[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*BOOK2*
*1*
Mintina goma da yin posting din maigidan ya kira ina d'aga waya ya fara fad'a cikin tashin hankali wai akan wane dalili zan zauna na yi dogon rubutu na 'batanci ga babban mutum irin Alhaji Tajo. Ashe wato duk ko'karin da yake yi mini bana gani kenan har sai na zartar da hukunci babu umarninsa. Na dinga ko'karin gaya masa cewa babu fa ta inda na 'bata mutumin kawai dai na tura sa'kona ne ta social media wanda nake ganin hakan zai sanya ya d'auki lamarin da muhimmanci. Bai saurare ni ba. Ya dinga fad'a cikin damuwa sai kawai na kashe wayar na zauna a wurin kuka mai karfi ya kwace mini. Wai ni ya zan yi ne. A ranar har gajiya na yi da amsa wayar mutane wasu na ganin beken abinda na yi, wasu kuma suna ganin hakan da na yi shine daidai, tunda yanzu rubutuna ya karad'e medi'a, kowa yana tofa albarkacin bakinsa akai.  Na tabbata kuwa sa'ko ya riski wanda aka yi dominsa.
Da maigidan ya dawo muka dinga musayar yawu duk akan rubutun da na yi. Yana ta tayar da jijiyar wuya wai na bashi kunya kuma idan masifar ta taso a kaina zata 'kare tunda wawa shine yake fad'a da mai kudi.
Jin cin mutunci ya fara biyo baya ya sanya na bud'e wuta. Na ce." Ba na tsoron kowa sai Allah. Kuma kudinsa ba zai hana na nemi hakkina ba. Na baka ha'kuri ka ki ha'kura duk hukuncin da za ka yi bai dame ni ba a yanzu rayuwar yarana ce a gabana."
Maganata ta k'ara tunzura shi. Kishi muraran ya bayyana a fuskarsa. A lokacin ne mai afkuwa ta afku ya ce." Ki je gida na sake ki saki daya tunda ke ba wanda ya isa ya gaya miki magana ki ji."
Na shiga rashin hankali mai tsananin gaske. Bakina ya dinga karkarwa ina so na bashi ha'kuri amma ya fice daga d'akin a gaggauce. Sai kawai na dinga nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un. Har zuciyata ta dan yi sanyi na tashi na fara had'a kayana cikin akwati. Ban tafi ba tukkuna sai da Yusi ya dawo daga makaranta.

Babanmu dai bai tsananta ba. Ya ce na share d'aki na zauna kafin kura ta lafa. Baba Sule ya zo da daddare ya dinga zazzaga mini bala'i wai na rikitowa kaina aiki, ga masifar nan na fara ga ni Alhaji Muntari ya sake ni, duk abinda ya biyo bayan rubutun da na yi zai k'are kaina.
Mamaki nake yi yadda suka d'auki lamarin da zafi. Wato na yi shiru kenan shine abinda kowa yake so. Saboda mutumin Yana da kudi duk abinda ya yi

daidai ne. Ni dai ban zage shi ba, ban fad'i mummunan magana a kansa ba, na fito ne na yi magana a matsayina uwa. Shine abin tashin hankali. Har yanzu ban tsorata ban kuma sa a raina cewa mutumin zai yi nasara a kaina ba.

Ban ta'ba ganin b'acin ran Sahura ba sai a ranar dan kirana ta yi a waya ta dinga yi mini fad'a wai me yasa ban yi shawara ba kafin na yi rubutun. Mahaifiyarsa ce bata da lafiya shiyasa a ka samu tsaiko.
Na ce."Sahura dukkaninku kun kasa fahimtar halin da nake ciki ko?  Kamalu yaro ne k'arami. Me kike tunanin zai faru a lokacin da aka had'a shi da garadan maza wad'anda suka jima suna aikata lalata. Za su koya masa wasu dabi'un marasa kyau, Sahura ki dubi azanci na da kyau, yau kusan sati uku kenan ana abu daya mutumin nan idan da Yayi niyyar yi wa yaran nan adalci daga can inda yake ma zai bugo waya ya ce a sake su. Amma kowa idan zai bud'e baki sai ya ce  za su samu sassauci to Ina adalci anan. Na yarda mahaifiyarsa bata da lafiya amma me yasa ba zai magantu ba yau kwanansa hud'u da dawowa ya kamata ya dubi lamarin da muhimmanci. Yadda yake cikin damuwa dalilin rashin lafiyar mahaifiyarsa mu ma iyayen yaran nan, haka muke cikin damuwa, a ganina wannan ce hanya mafi sau'ki da sa'kona zai riske shi. Amma ki je ki sake duba rubutun da kyau ki ga ni, ban zage shi ba wallahi."

"To ai kin kwatanta zagin 'kawata. Ba wai ka fito ka d'urawa mutum ashariya ba shine zagi. A a wasu kalmomin ma sun fi zagin muni. Kuma kin yi amfani da su wajan tura sakonki, babu tausasawa 'kawata mutumin nan fa ba yaro ba ne da shekarunsa, bayan haka kuma ke kanki kin san girma da daukakar da Allah Ya yi masa."

Na ce." Kin ga Sahura babu ruwana da wannan mafitata nake nema kawai. Ni kenan na zauna zuciyata ta yi bindiga saboda tunane tunane. Sahura koyaushe Ina gaya miki masu kudin nan fa ba su fiye bawa abinda ya shafi talaka muhimmanci ba. Sai sun ga sunansu zai 'baci tukkuna. Ina nan ina jiran abinda zai biyo baya. Wallahi yanzu na riga na bushe tunda babu irin masifar da ban gani ba. Ni da aure har abada."
Kashe wayar na yi sakamakon mugun kukan da ya kufce mini.

Ta dinga kira na kasa d'agawa saboda ba ni da wani karsashin da zan bata amsa. Kukan da ya jima yana ci mini towo a kwarya shi na dinga rizga kamar babu gobe.
Ummansu Hadiza ta shigo d'akin tana tana kiran sunana.

Kasa amsawa na yi saboda kukan da ya ci karfina. Ta ce." Ha'kuri za ki yi, kukan ba shine mafita ba, lamarin da ciwo da radadi a zuciya, to amma kowane bawa akwai k'addararsa, wasu a kansu, wasu akan abinda suka haifa, ki yi ta addu'a Allah Ya tsayar iya nan, 'kuruciya ce kowa da irin tasa."

Na ce." Ummansu Hadiza don Allah menene lefina anan? kawai dan na shiga media na nemi mafita sai kowa ya juya mini magana, shikkenan masu kudi sai su yi abu su kwana lafiya, talaka kuwa akan hakkinsa sai a nemi salwantar da rayuwarsa, kuma ace ba zai yi magana ba."

"Amina ba wai an hanaki magana ba ne, a a hanyar da kike bi da salon rubutunki wurin tura sakon shine abinda yasa iyayenki da duk wani mai k'aunarki shiga cikin damuwa, sanin kanki ne mutumin nan babba ne, to mai zai sanya ki rubuta masa wasika cikin izgili, ki watsa shi duniya bayan shi akayi wa lefi, idan hakan ya 'bata masa rai zai iya yin shiru. hukuma su ri'ke yaran sai baba ta gani kuma."

"Umma ba zaku fahimci yadda nake ciki k'unci ba ne, ba na iya rintsawa fa, ga Yusi kullum cikin koke-koke, sannan yaronan fa shine k'arami a cikinsu mai kike tunanin zai faru, ni wallahi har yanzu ban ga aibun abinda na yi ba."

Ta girgiza kai cikin jimami ta ce." Shikkenan to Allah Ya jishshemu alheri, idan k'urar ta lafa sai ki nemi mijin naki ki bashi ha'kuri dan gaskiya kin yi kuskure ba ki kyauta masa ba da kike zartar da hukuncin nan ba ki gaya masa ba alhalin Yana iyakacin bakin kokarinsa."

"Umma ku ajiye maganar Alhaji Muntari na gama aure har abada, ba zan koma gidansa ba."
Ta zuba mini ido na minti daya. Ganin babu rahama a fuskata yasa ta gyada kanta ta fita daga d'akin.

****
Kwana daya biyu uku har zuwa sati babu wata magana da ta 'bullo daga bangaran Alhaji Tajo. Dukda cewa kuwa sakon ya riske shi amma yau tsayin kwanaki bakwai kenan bai ce uffan ba. Hankalina ya Kai ma'kura wurin tashi, na rasa yadda zan yi da rayuwata babban tashin hankalina yadda ciwon damuwa yake nema kwantar da Yusi ni dashi duk mun zama zautattu. Hamusu kuwa kullum idan ya dawo daga kasuwa sai ya zo wurina mu zauna mu yi ta tunanin hanyar da za mu bi. Jin labarin Hamusu yana zuwa wurina ya sanya Alhaji Muntari kara yin fushi. Karin takaicinsa ma tunda na fito daga gidan ban kira shi a waya ba. Bayanin da ya yi wa Baba Sule kenan, ni ce na yi masa lefi ni ya kamata na neme shi na bashi ha'kuri, kuma yana da labarin bibikon da kanin tsohon mijina yake yi mini, dan haka muddin Ina son zama dashi sai na bashi ha'kuri kuma na kar'bi kuskurena."
Na cika da mamaki mutuka gaya a lokacin da baba Sule ya zo yana gaya mini yadda suka yi, dan shine yake ta faman bin sa yana bashi ha'kuri ya mayar da ni d'akina. Ban ja maganar ba saboda na riga na san halinsa sai na ce masa shikkenan zan kira shi na bashi ha'kuri. Na fadi hakan ne kawai dan mu rabu lafiya amma ba na tsammanin zan ta'ba kiran mutumin nan na bashi ha'kuri, babbar damuwata a yanzu fitowar yarona ba auransa ba.

Na kira Sahura cikin k'askantar da kai da nuna mata na kar'bi kure na, ban kyauta ba, amma ta yi mini hanyar ganin ogan nasu, ina son magana dashi baki-da-baki."

Ta ce." 'Kawata da tun farko ta wannan hanyar ki ke biyo abin bai zai yi tsamari da yawa ba. Tabbas oga ransa ya 'baci ainun da ganin sakonk'i, amma da yake mutum ne mai sanyin hali ya share bayan yana da hanyoyi da yawa da zai hukuntaki. Wallahi na fi ki shiga damuwa, amma tunda kin amsa kuskuranki, zan yi kokarin ganin mun samu ganinsa zan yi miki jagora."
Na ce." To shikkenan Sahura na gode sosai Allah Ya bar zumunci."

Bayan kwana biyu cikin farinciki Sahura ta kira ni take sheda mini ranar asabar ya ce mu same shi a ofis d'insa. Ta d'ora da fad'in." Kawata d'an Allah ki tausasa harshenki, ki kuma bashi ha'kuri bisa abinda ki ka yi, ba daidai ba ne ke kanki kin san haka. Kada ki tuno abubuwan da suka faru a baya tunda nema ki ke yi a wurinsa, kuma wallahi mutum ne mai adalci."
Na ce." Shikkenan Sahura zan yi kokarin yin hakan in sha Allahu rabbi."

Babanmu na samu na gayawa yadda muka yi. Ya ce." Hakan ya yi, ki je ki bashi ha'kuri sannan ki iya bakinki, wannan ya kara tabbatar miki da cewa ba a fad'a da mai kudi ko da kuwa kaine da gaskiya."
Ban ce masa komai ba na tashi na shige d'aki na kwanta abin duniya ya yi mini yawa.

Wannan littafin na kudi ne hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni gumina ba, hakki hakki ne komai k'an'kantarsa.
***

Ranar Asabar din da wuri na shirya. Yusi ma ya dira kuka sai na tafi dashi domin shi a ganininsa ai zuwa zan yi  na d'auko Kamalun dalilin da ya sa shi kuka kenan da na ce ba zan je dashi ba.
Nan Sahura ta zo ta same ni, na yi wa mutan gidan sallama muka tafi. Cikin adaidaita sahu ma dai sai kwakkwafata take yi akan na tausa harshena ina ce mata "To" Ganin yadda ta damu yasa na ce." Wallahi Sahura na fara zargin mutumin nan ba haka yake barin mutane ba, mussaman ma'aikatansa, kowa baya so a fadi lefinsa. Ko da shugaban kasa zan je na yi magana irin abinda za ki yi mini kenan, na gaya miki ha'kuri zan bashi fa'kat! Ni dai a fito mini da yarona kawai."
Ta ce." Ai kin ji irinta, ina ga ma tare za mu shiga ofis din kada ki zage shi dan ba k'aramin aikin ki ba ne."
Murmushin takaici na yi na ce." Kin san kuma wannan ba tarbiyata ba ce."
Ta yi shiru fuskarta duk ta nuna alhini. Yusi ya riko hannunta Yana fad'in." Umma idan mun je za su ba mu shi ko?"
Da sauri ta ce." I, in sha Allah d'an albarka."

Mun sami kimanin mintina talatin a zaune a reception kafin sakataransa ya fito ya ba mu umarinin shiga. Na tashi ina gyara mayafina. Sahura ta zaunar da Yusi a cinyarta tana fad'in." Ka zauna Mama ta shiga yanzu zata fito tare da Yayanka."
Sai ya zauna Yana murmushi. Na dubeta a tsanake na ce." Ki tashi mu shiga tare."
Kai ta girgiza mini. " Ki shiga kawai, Amina dan zatin Allah da d'aukakarsa kada ki ba ni kunya."
Jikina ya shika jin yadda take had'a da Allah. A sanyaye na kama hanyar ofis din gabana na bugawa da 'karfin gaske.

Na murda na shiga da sallama a bakina.
Ofis din babba ne sosai har akwai set din kujeru a can na hange shi a zaune da waya a hannunsa. Yana sanye da milk din shadda riga da wando babbar rigar dai tana ajiye a kusa dashi. Kamar koyaushe idansa sakaye da farin gilashi da ko a hoto baya cire shi.
Ya amsa sallamata a tsanake kana ya zuba mini idanuwansa wad'anda suke ko'karin kassara ni. Na fara dibi-dibi 'kafata tana lauyewa. Gashi ba wani jibgege ba amma sai cika da Ido da kwarjini. Don dai ni kaina a tsaye nake da addu'a ina ga da ba zan kai labari ba.
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE 🖊*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN🖊*

*TALLAH!*
 ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma

Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*BOOK2*
*2*
Da hannu ya nuna mini kujerar da take kallonsa. Na zauna a nutse cikin zuciyata ina ta buga masa tabbatyada. Shiru wurin ya yi. Sai sanyi da kamshi mai dad'i da yake ta surnanowa hancina.
Yana ta duban wayarsa Bai ce komai ba tun bayan amsa sallamata da ya yi. Na daure na k'askantar da murya tare dan risinar da kaina na furta." Ranka Ya dad'e ina kwana."
Ya dube ni fuskarsa kadaran kadahan. "Lafiya lau ranki shi dade, Amina Salisu mai hula, hakane sunan ko?"

"E, hakane Allah Ya taimake ka." Nafada tare da yin namijin ko'karin duban inda yake zaune.

Ya d'ora hannuwansa biyu akan table din da yake tsakiyarmu. Ya ce." Ina ta hasashen fuskarki ai."
"Ni 'kawar Sahura ce daya daga cikin ma'aikatanka, na yi mata rakiya ranar da za ta fara aiki daku a ranar kuma ka je duba ma'aikatar."

"E, tabbas kuwa na tuno ranar ni ma, ya jama'a, ya gwagwarmaya Kuma?"
Na dube shi Ina nazarin tambayarsa domin ta yi kama da ta rainin hankali. Sai kawai na yi shiru ban ba shi amsa ba.
Ya nisa kafin ya sake magana. "Me yake tafe dake yanzu?"
Na gyara zama sosai ina fuskantarsa domin dai addu'ar da nake yi dan samun rinjaye ta kawar mini da fargabar da na fara shiga dalilin kasantuwarmu wuri d'aya na ce." Akan maganar yaran da suka yi maka 'barna ne?"

Goshinsa ya d'an murza ya d'an lumshe idonsa duk Ina kallonsa. A kasalace ya dube ni. "Kina da aure ne?"

"A a ba ni dashi." Na bashi amsa kai tsaye.

"Bazawara ce kenan?"

Shiru na yi ban tanka masa ba domin ya fara ba ni haushi, zuciyata kuma ta fara rawa a kansa, ya ina gabas yana yamma, ga abinda ya kawo ni, yana yi mini wasu banzayen tambayoyi.
Ya koma ya kwantar da bayansa akan kujera ya rufe idonsa.

Minti kusan bakwai ina zaune kamar gunki bai ce mini ci kanki ba. Sai na dan bigi table din a hankali na ce." Allah Ya taimake ka ya ake ciki ne, ni ina daya daga cikin mahaifan yaran nan, kuma dai marayu ne iyayensu maza sun rasu, mune muke d'awainiya dasu, a yi hakuri a yi musu afuwa a kuma taya mu da addu'a. Allah Ya ba mu ikon cinye jarrabawarmu. Idan kuma kana ganin akwai takura a ciki to ka yi mana magana domin hukuma ta yanke musu hukunci sai hankalinmu ya kwanta."

Idonsa ya bud'e yana kashingid'en, Ya ce." Ai na yafe musu tuntuni, amma mai ya sa ki ka za'bi tozarta ni ta social media ta hanyar yin rubutu da kausasan kalamai a kaina, me na yi miki?"
Maganarsa ta farko "Ai na yafe musu." Ita ce ta ruguza kashi tamanin na zargin da nake yi masa.
A sanyaye na ce." Ka yi hakuri don Allah ban yi dan na wulakantaka ba, na yi hakan ne domin sa'kona ya yi saurin zuwa gare ka, amma ba nufi na na 'bata maka suna ba."

Murmushi kawai ya yi. Ya ce." Ban ji haushinki ba dalili akwai da dama masu bita da 'kulli da suka yi fiye da abinda ki ka yi, saboda haka kada ki damu kin ji ko."

"Na gode sosai, Allah Ya k'ara girma."
Ya amsa ''Amin Ya Allah."
Wurin ya sake yin shiru. Na daure na ce." To yanzu yaushe za mu tsammaci ganin yaran ?"

"A satin nan in sha Allahu." Ya fad'a yana kallona har sai da na tsargu."
Na risinar da kaina cikin girmamawa na ce." Mun gode sosai, Allah Ya saka da alheri, ya bawa Hajiya lafiya."

"Amin Ya Allah."

Tashi tsaye na yi ina dan gyara jakata dake rataye a kafad'ata.
Ya ce." Koma ki zauna ina son magana dake." Ban kawo komai ba na koma na zauna ina dubansa.

Iska ya fesar daga bakinsa yana duban tsabar idona ya ce." Ina buk'atar ki zama yarinyata, za ki dinga d'ebe mini kewa idan sha'awata ta tashi, ni kuma na yi miki alkawari duk abinda kike buk'ata na jin dad'in rayuwa zan yi miki."

Mamaki mai 'karfin gaske ya rufe ni. Tunda nake daga lokacin kuruciya har kawo yanzu da nake da shekaru sama da talatin a duniya babu wani mahalu'kin da ya ta'ba yi mini maganar banza irin wannan. Abu na biyu kuma sai mamakin yadda wannan furucin ya fito daga bakin babban mutumin da jama'a da yawa suka bada sheda cewar shi din mutumin arziki.
"Ina so ki zama yarinyata za ki dinga d'ebe mini kewa a duk lokacin da sha'awata ta tashi."
Maganar nake ta maimatawa a zuciyata ina mamakin ya aka yi har ya samu sararin yi mini ita. Shin ko yana yi mini kallon mutuniyar banza ne, ko kuma dan na zo neman alfarma a wurinsa ne zai fake da haka.
Shiyasa kenan da farko yake tambayata ina da aure ko ba ni dashi. Menene dalilin da ya sanya ake yi wa zawarawa kallon lalatattu ne? Me yasa a ka mayar da zunubin zina 'karamin alhaki a wannan zamanin.
Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wai ni yau wani namiji yake yi wa tayin zina.
Kafin na yi aune na ji maganarsa a kusa da ni. Na daga kaina Ina kallonsa yana tsaye daf da ni, ya yi mini rumfa hannuwansa zube a cikin aljihunsa.
Table din da yake gabana na buga da karfi na tashi tsaye tare da nuna shi da yatsa. Sai ya d'an matsa daga kusa da ni fuskarsa d'auke da mamakin yadda yatsana yake daf da karan hancinsa. Ammafa babu nadama a tattare dashi.

"Idan har sai ka yi fasikanci da ni tukkuna za ka bada umarnin sakin yaranmu to dan girman Allah ka sanya a rataye su, gobe a kawo mana gawarsu. Ina so ka sani neman mazan banza ba dabi'a'ata ba ce, kuma ba zan yi ba ko duk

duniyar nan za ka ba ni. Wallahi tallahi ka ji kunya, dattijo da kai kana yin wannan harkar ka tozartar da kanka, ka wulakanta nasabarka, sannan kuma ka yi wa Allah butulci wanda ya daga darajarka, ya d'aukaka, ya azurtaka da dukiya wanda nake da tabbacin cewa kai kanka ba kasan iyakarta ba. Ka cuce ni wallahi sai Allah Ya saka mini." Hawayen da nake dannewa suka zubo nasa hannu na goge.
"Ka matsa ka ba ni hanya na fice domin had'a numfashi dakai zunubi ne.
Yana tsaye turmin danya bai matsa ba, kuma bai ce komai ba.
Naja tsaki mai k'arfi da sauri na bi ta d'aya gefan zan wuce ya yi gaggawar tare mini hanya.

"Idan kin so abinda ya faru ni dake ki yi dogon rubutu kisa a fege d'inki na fece book. bai dame ni ba, idan kuma kin lullube to kamar kin haka rami ne kin binne mutuncinki. Dan haka ga hanya nan fice mini daga ofis."
Hanci na ja tsabar takaici da bakinciki ban iya mayar masa da raddi ba da sauri na murd'a kofa na fice zuciyata na wani irin ciwo dan wani kutittiran abu ne ya tokare mini a wuya.

Ganin yadda na fito a ki'dime ya sanya Sahura da Yusi tashi tsaye. Ita tana tambayata abinda ya faru. Shi kuma ya rike hannuna yana tambayata ina Kamalu.

Da 'kyar na iya furta sunanta." Sahura mu je kawai."
"Sis me ya faru ne? Ya kuka yi dashi?"
Cikin tsawar da ban san lokacin da na yi ba na ce." Don Allah ki wuce mu tafi na ce miki."

Yusi ya rushe da kuka Yana fad'in." Mama kin ce zaki taho da Yayana to yana ina?"
Yaron kuka yake tu'kuru yana daddagewa, haushi ya sake kama ni.
Bud'ewa kofarsa ya yi daidai da lokacin dana gaura masa mari wanda tunda ya zo duniya ban ta'ba yi masa irinsa ba. Sai ya gigice! ya kidime domin abin ya zo masa a bazata! ya rasa Ina zai nufa kawai sai ya nufe shi a guje ya rirrike hannuwansa yana rusa kuka na fitar hankali.

Kawar da kaina gefe guda na yi zuciyata in banda za'babbaka babu abinda take yi.
Ya k'araso wurin da muke tsaye ni da Sahura wadda take ta faman yi mini fad'a akan marin yaron da na yi.
Sai da ya iso tukkuna ta ta dan risina tana gaisheshi.
Ya ce." Ashe tare kuke?"
"E, ranka ya dad'e don Allah ka yi hakuri.

"Me kuka yi mini?" Ya fad'a yana kallonta. Shiru ta yi ba tace komai ba.
"Wannan yaronta ne?"
Ya yi maganar cikin 'bacin rai."

Da sauri ta ce." E, kanin Kamalu ne."
Abin mamaki sai yasa hannu ya d'auki Yusin din yasa a kafadarsa yana d'an jijjigashi kamar yaron goye. Ya dube ni.
"Idan ba kya so ni ki bar mini shi. Wannan marin da ki ka galla masa ko ni ki ka yi wa irinsa sai na gigice, ke fa ki ka haifi abinki."
Kallonsa na yi muka had'a ido. Yanayin yadda yake maganar shine ya tabbatar da ransa ya baci.

Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Ki dubi yadda yake ajiyar zuciya mugunta ce wannan tsagwaronta. Ko ba haka ba ne?" Ya fad'a yana kallon Sahura.

Da sauri ta ce." Ni ma fad'an da nake yi mata kenan.
Ya juya da yaron a kafad'arsa. Ofis d'insa ya shige dashi.

Sahura ta kalleni jiki a mace ta ce." Wai don Allah me ya faru ne na ga kin fito a fusace! Ni fa jikina duk ya mutu wallahi."

Sahura ki bari kawai wannan mutumin bashi da hali wallahi. Mutumin banza ne.
Cikin zare Ido ta ce." Mutumin banza kamar Yaya?"
"Ki bar maganar kawai Sahura amma Allah sai ya saka mini."
Ina rufe baki suka fito daga ofis din.
kudi da wani irin biscuits ne a hannun Yusi. Ya dubi Sahura cikin nutsuwa ya furta." In sha Allahu ranar litinin jibi kenan zan sa a kawo muku yaronku har gida, Allah Ya kiyaye faruwar haka anan gaba."
Cikin tsananin farinciki ta fara godiya. Bai tsaya amsawa ba ya bar wurin. Ganin haka ya sanya ni ma na kama hanyar fita ina mamakin abinda ya yi babu wanda zai yarda da cewa shine mai neman keta mini haddi.

Ta biyo bayana hannunta ri'ke dana Yusi  har tana had'awa da dan gudu domin na yi masu nisa daf nake da fita daga wurin. Ta iske ni tana dan sauke ajiyar zuciya.
Ban dubeta ba hankalina yana kan tsayar mana da abin hawa.  Zuciyata a takure, gabad'aya sai duniyar ta fice mini daga rai ganin yadda rayuwar ke garaaranba da ni.
Har muka shiga adaidaita sahu  tana ta tambayata abinda ya faru a tsakanina dashi. Na yi shiru ban ce mata komai ba. Sai ta ajiye maganar ta fara kwarzanta kyawun hali da nagartar da ya nuna mana. Nan ma ban ce mata komai ba, tana gaya mini kudin da ya bawa Yusi har da dala irin ta amarica biyu a ciki bayan naira dubu sha bakwai data lissafa. Na dubeta tare da furta." Za ki wuce gidanki ne, ko za ki je ku gaisa da su mama.
"Mu je can gidanku Amina akwai maganar da zamu tattauna."
D'auke kaina na yi ban sake magana ba har aka sauke mu, ita ta bada kudin motar muka wuce kamar wasu kurame, yanayi na gabad'aya ya sagar mata da guiwa. Sai satar kallon fuskata take yi.

Muna shiga gidan Yusi ya ruga d'akin Ummansu Hadiza da gudu yana gaya mata ranar litinin Kamalu zai dawo. Sai gasu gabad'aya sun fito tsakar gidan da murna a tare dasu.
Sahura ta tsaya tana yi musu bayani. Ni kuma na bude d'aki na shiga ina jinsu suna ta fad'in." Dama ai an shedi mutumin yana da kirki kwarai da gaske, suna ta gode masa.
Na nemi wuri na zauna, har yanzu kafafuna ba su daina rawa ba. Duk lokacin dana tuna k'azamar maganar da mutumin nan ya yi mini sai na ji kamar na rushe da kuka. Na dinga duban jikina, wai ko zan ga alamar karuwanci a tare da ni.  Babu ko daya domin dai shigar mutunci nayi mayafina mai kauri da fadi ya rufe mini kaf ilahirin jikina. D'inkina kuwa riga da zani ne na atamfa. Babu wata alama ta 'karanta ko rashin kamun kai a tattare da ni.....✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da

kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*BOOK2
*3*
Hawaye masu d'umi suka kwaranyo mini a kumatu. Sahura ta shigo ta same ni a haka, na kalleta sai zuciyata ta sake tsinkewa. Hawayen suka tsananta zuba. Ta zauna kusa da ni tare da ri'ke duk hannuwana biyu.
"Kawata d'an girman Allah ki gaya mini menene, ko wani abun ya yi miki da ki ka shiga, kin san shaidan ba abinda ba zai aikata ba.

Hancina na ja. Hawaye gaja-gaja a kumatuna na ce." Sahura mutumin nan nema na ya yi da fasikanci wai na zama yarinyarsa, wallahi tallahi ban yi masa sharri ba. Sahura dan Allah me ya gani a tare da ni wanda ya nuna masa ni 'yar iskace."

Jikinta ya yi kwatakes ta dinga kallona gabad'aya ta gaza yin magana tsabar mamaki da rud'ani.
Na sake yan majina a karo na biyu  "Na fad'a masa idan har sai ya yi fasikanci da ni zai fito mana da to yara, ya sa a rataye su kawai."

"Kawata na yarda ba za ki yi masa sharri ba. Na san halinki, duk kiyayyar da kike yi masa haka kawai ba za ki kirkiri abinda bai yi ba ki ce yayi, Amma don Allah maganar nan ki barta kada ki gayawa kowa, ni ma na yi miki al'kawari babu wanda zai ji. Kin san idan kin fito kin fad'a wa duniya ba yarda za a yi ba, karshe ma ki jefa kanki a masifa, ki kyale shi da halinsa. Tunda dai Allah Ya tsare ki shikkenan, amma zahiri na girgiza da jin wannan batu, wato Allah A zahiri fir'auna a zucci. Kai amma mutumin nan ya
ba ni mamaki wallahi."

Hannu nasa na goge kumatuna. Jiki a sanyaye na ce." Babu wanda zan gayawa ai, in sha Allahu sai Ubangiji Ya bi mini hakkina, na bar shi da Allah, idan halinsa zai bayyana kowa ya ga sani".

Sai yamma can Sahura ta tafi dan ko gidansu bata shiga ba saboda daf ake da kiran sallah magariba.
Ina idar da sallah Hamusu ya shigo, nan muka zauna muna tattauna maganar. Yana gaya mini ai tun yana kasuwa ya samu labari. Alhaji Tajo din da kansa ya sanar a shafinsa na fece book. A lokacin 'yan jarida suka samu abin yayatawa amma inda gizo ke sa'kar ba duka yaran ya bada umarni saki ba, Kamalu ne kawai, hakan sai ya janyo cece-ku-ce a kafafan sadarwa. Ni dashi muka yanke shawarar da muke ganin itace mafita a garemu baki daya. Makarantar horo da ladabtarwa zamu aika dashi dake can k'aramar hukumar k'iru.
Dama gwaggwo ce abin ji, amma jin hukuncin Allah da muka gaya mata sai ta sake k'arfafa guiwar yin hakan. Na gayawa Babanmu shima ya bada goyan baya tare da fatan alheri.
don haka ana sako yaron da kwana uku muka gama had'a masa komai yana kuka da komai Hamusu ya tasa k'eyarsa domin kai shi makaranta. Cikin zuciyata na bi shi da fatan alheri da addu'ar Allah Yasa karshen fitinarsa kenan. Ina kuma yi masa addu'a Allah Ya sa ya zama kangaran, mahaddacin al'kur'ani mai girma.
tun Yusi na kuka da damuwa har ya warware. Saboda Ina gaya masa d'an'uwansa yana can makaranta zai zama babban malami, sannan ba zai yi almajiranci ba, sa'an nan kuma ba za a daure masa kafafu ba. To
sai ya kwantar da hankalinsa domin yadda na lura babbar matsalarsa a ce Kamalu Yana bara, irin yadda ya ga wasu al'majiran ke yi.

****
Kwanaki suka shud'e aka fara lissafin wattani babu wata 'kwakkwarar magana daga 'bangaran Alhaji Muntari. Har yanzu shi a zaman da ake yi na kira shi na bashi ha'kuri. Gashi har na yi jini uku, na yi iddah bai ce komai ba Baba Sule yayi masifar har ya gaji. Idan ya zo gidan ma ko gaisuwata baya amsawa.
Hankalina ya kwanta. Ba ni da wata fargaba a yanzu. dama Kamalu ne to Alhamdullahi makarantar da aka kai shi muna samun labarin sauyin rayuwar da ya samu sosai daga bakin malaman. Sai na cigaba da gudanar da

harkokina kamar koyaushe na fitar da kudi masu yawa na sayo atamfofi masu tsada da shaddodi har da leces na tayar da jari na kaina.
Sai da na kammala din'kunan tukkuna na kira Ya Falmata a waya na gaya mata zan an aiko da kaya. Ta ji dadin haka kuwa dama nemansu ake yi, mussaman wadda take take turawa a Abuja ta kirata a waya ya kai sau nawa.
Ko sati daya ba a yi ba, kayan suka kare Ya Falmata ta had'a mini kudina tsaf dubu dari takwas ta tura mini. Tare da buk'atar wasu.

Na kira Hamusu kan maganarmu ta kwanaki ya nemo mini shago mai yalwa wanda ya kasance a bakin titi zan kama haya sannan ya samu mini k'wararrun teloli da suka iya d'inki na gida da na waje mussaman irinsu sinigal mali da nijar.
Samun telolin bai yi wahala ba, nan da nan aka same su dan har sun haura adadin dana buk'ata.
Shagon ne duk wanda za a samu sai a loko, ni kuma na fi son na bakin titi. Sai ya cigaba da nema cikin ikon Allah aka samu amma yana hade da gida. A titin kuntau. Kuma maigidan ya ce ba zai bada hayar shagon kadai ba dole sai da gidan dubu dari uku a shekara.
Na je na duba wurin, al'karya ce ta jama'a, kuma unguwa ce ta masu hannu da shuni, Ina ganin za a samu alheri a wurin.
Na yi shawara da Babanmu ya amince. Na kira anti Yagana ma na gaya mata ta yi mini fatan alheri.
Sai kawai na roki Allah sa'a, na biya kudin. Karin farincikina ma shagon kato ne zan iya zuba kekuna sama da biyar a ciki.
Zuciyata ta fara raya mini wani abu, hakan ba haramun ba ne, sai dai illar dake ciki, da kuma fassarar da jama'a za su yi mini akai. Allah Ya rufa mini asiri a yanzu na bawa miliyan biyar baya kuma neman kudin nake yi, ba a san abinda gobe zata haifar ba. D'akin da nake bashi da yalwa ga zafin tsiya, Ina ganin zan komai gidan da shagona yake sai na samu 'yar tayin zama. hankalina zai fi kwanciyar da hakan. Ina kallon duk abinda yake faruwa ba, bayan haka zan samu saukin zurga  zurga tunda ba ni da abin hawa.
Wannan shawarar ita na gayawa Babanmu. Ya jima yana dawurwura kafin ya amince. Na ce zan tafi da Usaini. Sannan zan nemi alfarma Sahura ta ba ni Yusura.
Da kawu Sule ya ji sai ya hau fada yana cewa na yi arziki zan guji gida na tafi uwa duniya na yi zaman kaina. Allah ya ce Annabi ya ce, dole idan zan tafi na d'auki daya daga cikin yaransa mata.
Na ce hakan ba matsala ba ne Fiddau ta shirya kayanta sai mu tare gabad'aya.
Itama Sahura bata musanta mini ba, ta ba ni Yusura har tana cewa babanta ya ce ya bar mini har auranta. Na yi dariya sosai ina fad'in Allah Ya ba ni ikon sauke nauyi.

Cikin ikon Allah komawata kuntau sai ta fashe mini. Domin na nemi sa'a a wurin Allah, na kuma mika masa al'amura  ya kuma dubi zuciyata.

Harkoki suka bud'e mini  neman kudin nake yi haikan. Bayan manyan dinkun nan da nake yi ana fitar mini dasu. Har zannuwa Ina sayarwa. Na sanya aka yi mini singbord mai d'auke da tambarin shagona A&A fashion designer wato (Amina Aminu kenan)  a jikin bannar din hotona ne cikin ado da kwalliya irin na mutanan nijar da sinigal sun yi masifar kyau. Wani irin jiki ne da ni mai d'aukar ado  babu wanda zai ce na ta'ba aure balle yara biyu.
Singbord daya aka sanya shi a farkon titi. Na biyu Kuma aka sanya shi a kusa da shagon.
Hakan sai ya k'ara haskaka lamarin. Cikin unguwar da sauran dake makotaka da ita suka fara kawo mana aiki.

Ba na kwatanta yin hakan akan Fiddau da Yusura dalili iyayensu Amana suka ba ni. Kuma 'yan mata ne, akwai mutanan da ba su da fahimta. Hankalina bai kwanta ba sai da na tabbatar sun  cigaba da karatunsu, boko da islamiyya duk makarantun kudi ne har Yusi. Sune dai suke yi mini hidimar gida idan sun dawo, Usaini kuma yana tare da yaran shagona.
Ni kuma aikina tallata kasuwancina a kafafan sadarwa. TikTok fece book Instagram Whasap da sauransu.  Sutturuna suka yawaita dalilin fashion din da nake nunawa a duniya bagraoud muke samu a cikin gidana mai kyau a yi mini hotona masu kyau cikin dinkuna kala kala na watsa a Media tare da lambobin wayarmu da location dinmu.
Hakan ya kar'bu mutuka gaya dalilin kyawun suffata. Duk kayan da na sanya sai sun zauna mini.
Kafin wani lokaci na tara followers na ban mamaki. Sai ya zamana 'yan film suka mayar da shago da gidana sansaninsu.

Jin haka hankalin Babanmu ya tashi ainun! Takanas ya zo da sassafe ya rufe ni da fad'a irin wanda bai ta'ba yi mini irinsa ba.

"Amina kada ki ga na zuba miki Ido ki nemi ki zubar mini da mutunci a duniya. Ina samun labarin duk irin abinda kike aikatawa. Wato watsa hotonanki da kike yi media hakan bai wadatar ba har sai kin had'a guiwa da 'yan film me kike so ki zama a duniya, Ashe shine dalilin da ya sanya ki ka nemi da ki kebance ke kad'ai domin ki yi abinda ki ke so ko? To ki kiyayeni wallahi, zan sa'ba miki muddin baki daidaita hankalinki ba, ni ba zan yarda ki juya ni ba don kina ri'ke da gidana hakan ba zai sanya na zuba miki Ido ki zubar mini da mutunci ba."

Duk yadda na so Babanmu ya fahimce ni ya ki sauranta. Ransa a b'ace ya tafi domin ko abinci ma bai zauna ya ci ba.
Na kira anti Yagana na gaya mata duk yadda ake ciki. Ni dai 'yan film din nan ba ni nake gayyatosu ba, zuwa suke yi su kawo aikinsu.  Ta ba ni shawarwari masu yawa da kuma addu'oi. Wannan fad'an da Babanmu ya zo ya yi mini akwai sanya hannun mak'iya sune suka tunzura shi, amma dai ta jadadda mini cewa na kiyaye sosai na kuma yi takatsantsan.

Ban fasa tallata kasuwancina ba, amma na kiyaye mu'amulata da 'yan film d'in tunda hakan zai janyo mini matsala.
Allah buwayi gagara misali. Wato duk lokacin da Ubangiji yace kasance akan bawa babu mahalu'kin da ya isa ya dakatar. Zuwa yanzu na bud'e shaguna uku biyu ana hada hadar dinkuna dayan kuma cike yake da zunnuwa mayafai da takalma. Hamusu shi yake ri'ke da shagon zannuwan yayin da Usaini yake tsaye akan biyu.
Na yi k'arfi sosai Allah ya yi mini abinda dole na gode masa. Gidan da nake ciki maigidan ya siyar mini dashi miliyan shida da dubu dari biyu. Abinda nake dashi a yanzu sun haura miliyan ashirin bayan jarin da nake juyawa. Wannan dalilin ya sanya na yanke shawarar biya mana umara ni da Babanmu domin ina so na je d'akin Allah na yi godiya a gare shi.
Ranar dana gayawa Babanmu na biya masa umara da Azimi zamu tafi sai ya fashe da kuka. Yana fad'in." Amina ashe ina da rabon zuwa makka. Ashe a jikinki zan huta Amina, kin ri'ke mini gida, kina kula da ni, kin hana ni shan wahala. Yau kuma kin yi mini albishir din zuwa d'akin Allah. Amina ina ro'kon Allah ya yi mini albarka. Ya bunkusa kasuwancinki ya yara mini zuriararki. Burina a duniya ki yi aure Amina domin Ubangiji ya gama yi miki komai na Jin dad'in duniya."
Na ce." Baba ka daina kuka, duk abinda na zama a duniyar nan kune sila. Aure kuma lokaci ne idan ya zo dole ne zan yi ko ina so ko ba na so, ka yi tayi mini addu'a dai."
Har na baro gidanmu Babanmu bai daina ya sanya mini albarka ba. Matan gidan kuwa kowacce ta watsar da makamanta, idan na je kamar zuma kowa yana so ya jingina da ni.

****

Uku ga Azimi muka tashi zuwa kasa mai tsarki. Fiddau da Yusura kowacce ta tafi gidansu. Domin zamansu su kadai a gidan bai dace ba, dalilin da ya sanya kenan na ce su je gida idan na dawo sai suma su dawo, dama an yi hutun makaranta..

Tunda muka isa kasa mai tsarki koyaushe ni da Babanmu muna harami, dan shi wasu lukutan ma anan yake kwana ni ce nake komawa masaukinmu. Sai dai da safe idan na je na same shi.
Godiyata ga Allah bata yankawa kafin na fara rokar wani abu sai na yi godiya bisa ni'imar da ya yi mini. Sannan na shigar da bukatata. Miji nagari shine burina a yanzu wanda zai ri'ke ni tsakani da Allah ya kuma ri'ke yarana. Ban wuce aure ba kamar yadda kowa yake gaya mini, to idan Allah ya kaddara mini dole sai na 'kara wani auran a duniya ina rokansa ya azurta ni da nagari wanda mutuwa ce zata raba.
Wannan addu'ar ita nake ta nanatawa hannuwana dafe da ka'aba hawaye na kwaranyo mini.

Kunnuwana suka jiyo mini sautin kukan dattiijuwa tana fad'in." Allah wannan yaron bawanka ne, kafi ni sanin abinda yake lullube a cikin sha'aninsa. Ka yi

masa komai a duniya Allah ina ro'konka ka bashi ikon duba matar da zai raya sunna da ita. Allah idan bashi da lafiya ta wannan fannin Ubangiji ka bashi lafiya. Ya rabbi Allah idan asiri akayi masa matansa suke mutuwa Allah ka kawo karshen lamarin nan. Ya Ubangiji Allah Ina da buri a duniyar nan kafin ka d'auki raina naga yaran wannan yaro. Allah Ka kawo karshen wannan lamar........Bata k'arasa ba wata mata dokekekiya ta bangajeta duk a kokarinta na zuro hannunta ta dora a kan ka'aba. Abinka da jikin tsufa babu kwari a take ta zube a kasan wurin. Da saurin gaske na bi ta na kamata ta tashi da kyar tana numfashi. Wata mace mai kama da ita ta kutso wurin ta ri'ke gefan kafad'arta tana fad'in." Hajiya sai da na ce miki kada ki shiga jikinki babu kwari, kuma wasu mutanan ba hankaline da su ba. Allah yana jinki a duk inda za ki yi addu'a."
Na ce." Wallahi wata mara hankali ce ta bangajeta, kuma ba ta san ma ta yi ba."
Muka fito sarari da ita kekenta yana can gefe muka zaunar da ita a akai sai numfashi take yi da alama ma bata da cikakkiyar lafiya.

"Sannu fa mun gode sosai ."
Murmushi kawai na yi. Na juya da niyyar barin wurin sai na tsinkayi maganata a karo na biyu bayan godiyar da ta yi mini.
"Kamar na san fuskarki, kina yin film ko?"
Girgiza kaina na yi. "A'a ba na yin film Hajiya."
"Amma dai  kamar Ina ganin hotonanki na yawo a kafafan sadarwa mussaman Instagram da TikTok fece book da sauransu."

Babu wata damuwa na ce." E, ni ce, Hajiya Amma ba na film Ina gudanar da harkokin kasuwanci na ne a sahar."
Ta girgiza kanta da murmushi a fuskarta ta furta." To Allah Ya taimaka ya bada sa'a, idan kina neman wata gudumawa sai ki neme ni zan baki lambar wayata. Sunana Hajiya Saratu Ibrahimu 'Danbatta."
Gabana ya fad'i. Tsira mata Ido na yi na 'yan sakkoni, ashe kallon tsoro na yi mata da farko sai yanzu na hangi kamarsu daya da Alhaji Tajo.
Jikina ya mutu sosai. Ashe dattijuwar mahaifiyarsa ce. ita kuma wannan din diyarta ce.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*

□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177

CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*BOOK2
*4*
"Ko za ki ba ni lambar wayarta ki ne."
Maganata ce ta dawo da ni hankalina. A didirirce na ce." To bari na baki." Ban kawo komai a raina ba na fara fad'a mata lambata ta yi serving tana fad'in." Ke yar wane gari ce? Mu dai 'yan Kano ne."
"Na ce." Ni ma 'yar Kano ce, an haife ni a cikin unguwar kabuga."
Maganar Hajjan tasu ta d'auki hankalinmu ni da ita gabad'aya ina take fad'in 'Yar nan shin kina da aure ne?"
Tambayar da ta yi mini kenan. Gabad'aya sai muka zuba mata Idanuwanmu.
"Murmushi Hajiya Saratun ta yi kafin ta ce Hajja kenan, har na fahimci abinda yake kasan zuciyarki."
Shiru muka yi gabad'aya ni dai haka kawai sai na ji gabana na bugawa.

Hajiya Saratun ta Nisa cikin wani yanayi kafin ta cigaba da cewa "Kin yi wa mutumin sha'awarta ko? ke duk maccen da ki ka gani sai ki ce kin yi wa Tajo sha'awa, shi kuwa wannan ina ga haka zai koma ga Allah bai yi aure ba."
Da saurin gaske ta furta." Bakinki ya sari danyan kashi Saratu, wai mai yasa ke ba ki iya magana ba ne, kada ki manta fa muna cikin kasa mai tsarki gaban ka'aba, amma kina nema ki jefi d'an-uwanki da baki irin haka."
Cikin dariya ta ce." Allah Ya baki ha'kuri Hajjata."
Sai ta kalle ni.
"Amina kina da aure ne? Hajja tana tambayarki.
Lokaci guda bakina ya fara rawa, dan wani bala'in kwarjini suka yi mini......."A a yanzu dai bani dashi amma ina shirye shiryen y......"Ai ba a daura ba ko?"
Hajja ce ta katse ni."
Na ce." E ba a daura ba Hajiya amma an kusa."

Sai ta riko hannuna katamau! " Don Allah ki auri Tajo kin ji 'yar nan, na yaba da hankalinki, kuma duk na ji irin addu'oin da ki ke yi akan neman miji nagari, ki sanya a ranki adduarki ta kar'bu shiyasa Allah ya hadamu anan, don Allah don Annabi ki taimakeni ki auri yaron nan kin ji ko."
Gwiwa ta dinga rawa kafafuna sukayi mugun sanyi jin yadda matar take ta hadani da girman Allah har jikinta na rawa. Muryarta na wani irin karkarwa wai sai na amince tukkuna zata sakar mini hannu.
Hawaye suka kwace mini da rawar murya na ce." Hajiya ni ba budurwa ba ce bazawara ce, aurena biyu, ina da yara biyu, sannan ba a auran na taso a gaba ba, neman kudi nake yi duk domin iyaye da yarana, don Allah ki yi hakuri ku bar maganar nan."

Sai kawai itama ta fashe da kuka. Tana ce wa." Ai taimako na ce ki yi, duk abinda kike buk'ata na rayuwa kin samu a wurin Tajo, ni na haifi abina wallahi bashi da matsala, lafiyarsa lau, kaddara ce kawai take d'awainiya dashi, amma in sha Allahu daka kanki komai ya zo karshe "

"Hajja wace irin rigima ce wannan, dan Allah ki sakar mata hannu, kada hankulan mutane ya dawo kanmu, dole sai an bi komai a hankali, idan Allah ya kaddara sai ki ga an yi amma ba wai yanzu a tursasata amincewa ba."

Gabad'aya muka dubeta a lokacin da take maganar ni ina can tunanin abubuwa masu yawa. Mahaifiyarsa tana nan tana shaidarsa mutumin kirki ne, bata san manemin mata ba ne.
"Saratu haka kawai na ji yarinyar nan ta kwanta mini a raina, na tabbata addu'ar da na yi ce Allah ya kar'ba a take, ko kina so na mutu banga abinda Tajo zai haifa ba."
A sanyaye ta ce." Ina so mana Hajja, amma kamata ya yi a bi komai a hankali."

Duk maganar da suke yi hannuna yana cikin nata ta ri'ke kamatau! da kyar na furta." To shikkenan Hajiya zan yi shawara in sha Allahu, duk abinda muka tattauna da mahaifina sai na sanar daku."
Ta sassauta rikon da tayiwa hannuna Kin tabbata."
Kaina na d'aga mata tare da furta"In sha Allahu rabbi, na yi hakan ne domin ta cika ni ba wai don na amince da bukatartata ba.

Maganar da Hajiya Saratu take yi a waya itace ta d'auke mana hankali gabad'aya.
"Cikin dariya take fad'in." Ga mu nan a tare ai ta samu wata yarinya wai dole sai ta aureka tana nan ta ri'ke ta tamau don rigima, to kai Tajo ai ka yi mata kuma."
Da yake hands free ne muna jin muryarsa yana fad'in." Matar aure kuma a ina?"
Ta ce. Anan muka had'u da ita, ni ma kuma na yaba gaskiya na yi maka sha'awarta."
" Ku ajiye maganar nan Saratu, kada ku kawo 'yar mutane ta rasa rayuwarta, na ha'kura da auren nan fa, ba ni ma sha'awarsa gabad'aya."
Abinda ya fad'a ya daga hankalin mahaifiyartasa ta kar'bi wayar ta fara yi masa fada akan me zai sa ya furta haka.
Ha'kuri ya dinga bata har ta sassauta. Yana fad'in." Ina sa ran yau da daddare zan shigo garin sai na ga matar na amince, indai hakane burinki Hajja."
Ta juyo tana kallona." Kin ji shi ya amince ko, kema kin amince ko Amina?"
Shiru na yi ban iya furta komai ba, kawai Ina mamakin karfin hali, da rikici irin na tsufa. Haka kawai daka ganin sarkin fawa sai miya ta yi zaki. Ni abinda ya fi d'aga mini hankali ma yadda duk matan da ya aura suke mutuwa. Ta ya za a yi Ina ji Ina gani na kashe kaina, akan wane dalili, tabbas

dana san taimakon da na yi mata haka zai janyo da na yi gaggawar barin wurin ban tsaya mayar da magana da su ba.
Babanmu na hango Yana zuwa wurin da muke tsaye.
Yana karasowa na ce." Hajja  ga Babana nan tare muke da shi." Da sauri ta saki fuskarta. Na ce." Baba wannan mahaifiyar Alhaji Tajo ce wannan dan kasuwar, ita kuma wannan 'yar'uwarsa ce."
Cike da girmamawawa ya gaisheta ya d'ora da fad'in." Mun gode sosai da karamancin da akayi mana, Allah Ya saka da alheri, ai yaro ma tuni muka tura shi makaranta yana nan ya shiryu yana ta yi wa al'kur'ani hidima."
Ita dai murmushi take yi don bata gano akan abinda yake magana ba.
Hajiya Saratu ta ce." Kada dai ki ce kuna da alaka da yaron nan Kamalu wanda ake zargin sun yi masa b'arna a kamfaninsa wattanin baya"

Babanmu da sauri ya ce." E, itace mahaifiyarsa ai, yaranta biyu marayu ne ubansu ya rasu, sai Allah ya jarrabi babban da fitina ake ta fama dashi, amma dai yanzu alhamdulillahi."

Girgiza kai Hajjan ta yi ta ce."  Lallai akwai shirin Allah a cikin al'amarin nan, shiyasa ya shirya haduwarmu a wuri d'aya, idan an jima Tajo din zai sauka, idan ya so sai ku zo masaukinmu ku same mu domin akwai muhimmiyar maganar da zan tattauna da ku."

Babanmu fuskarsa ta yalwata da fara'a, irin wanda na jima ban ga irinta ba, tun kafin ma ya ji akan abinda ake nemanmu, sai godiya yake yi. Ni dai Ina tsaye sai kace dasashen itace babu abinda yake aiki a jikina sai zuciyata. Domin babu irin sa'ke-sak'en da ba ta yi mini, wai shin me yake shirin faruwa da rayuwata ne?" Ba zan ce da na sani ban zo ba, amma hankali ya tashi ainun ganin yadda jikin Babanmu yake rawa, a hanyarmu ta zuwa masauki yana ta Addu'a Allah Ya sa alheri ne.

Farincikin da mahaifina ya shiga shi ya kara sagar mini da gwiwa na dinga tunanin hanyar da zan bi wurin ganin na yi wa al'amarin da yake shirin tunkaro ni tutsu.

Daf da magariba baba ya sake komawa massalaci domin yin sallah. Ina kallonsa ban yi yun'kurin bin sa ba dalilin rashin karsashi da kwarin jiki. Zuciyata babu irin sake-saken da ba ta yi mini na zuwana garin. Tana raya mini dana san abinda zai faru kenan da ban zo ba.
Matar nan da gaske take nema take yi ta 'ka'kaba mini d'anta wanda babu shi kwata- kwata a tsagin rayuwata. Bai yi mini ba, baya burgeni ko kad'an, kudinsa kuma babu su a gabana. Ina so na samu namijin da Yayi daidai da ra'ayina, mai rufin asiri daidai gwargwado. Wanda yake da ilimin zamantakewar rayuwa da fahimta kamar Yaya Aminu. Amma me za a yi da irin auran su Alhaji Muntari da Tajo, a ganina babu ci-gaba sai dai koma baya.

Auran nutsuwa da kwanciyar hankali ya fiye mini auran sanannan mutumin da duniya ta suturtashi da arziki a zahiri, amma kuma a badi'ninsa mutumin banza ne.
Yadda ake masa kallo kamili babu wanda zan fito na gayawa abinda ya aikata mini ya yarda. Shiyasa barin maganar a cikina ta fiye mini alfanu.

Yanzu dai babbar damuwata yadda zan sa'bule ba tare dana 'batawa Babanmu rai ba, uwa uba waccan matar da ta kwallafa rai a kan na auri d'anta.

Ringing din wayata ya katse mini tunani lamba ce sabuwa kuma special irin ta manyan mutane. Zuciyata na harbawa na daga wayar da sallama a bakina. Muryarta ta karad'e mini kunne.
'Yarinyar kirki Mamanki ce, ai ni na cewa Saratu ta sanya mini lambarki sai mu yi magana, za ku zo ko?"
Duk lokacin da matar za ta yi mini magana nakan rasa kuzari a tare da ni, uwa uba bakina ya kan yi mini nauyin furta mata maganar dana san zata bata mata rai.
Da kyar na iya furta." Baban namu Yana massalaci Hajiya."

"To kin ga Tajo din ma ya iso muna nan a tare ku kadai ake  jira, ai shi ya amince ya ce ma ko gobe a daure sai a nemi albarkar ranar tunda Juma'a ce."

Gabana ya dinga duka! Na shiga rawar baki da kyar dai na iya furta."Hajiya don Allah ki yi hakuri kada ki ce na yi miki gardama wallahi ban shirya aure yanzu ba, akwai muradaina da yawa da nake so na cika, kuma ko bayan haka ma mutumin nan ya fi karfina, ni din ba kowa ba ce, haka zalika mahaifina ma ba kowa ba ne a duniyar nan."

Murmushi ta yi a hankali ta ce." Yanzu nan Saratu ta gama yi mini bayani a kanki,  mu ba mu kyamaceki ba Amina, me zai sanya ke ki kyamace mu, Tajo gashinan a zaune da bakinsa ya furta Yana sonki domin Shima ya yaba da dabi'unku, kada ki sanya wasu tunane tunane a ranki in sha Allahu alheri ne auran nan naku."

Bakina ya mutu na kasa cewa komai. Ina dai jinta tana sake kashe mini jiki da nasihunta.Wasu hawaye masu d'umi suka fara tsiyaya a kumatuna . Wai shin wace rayuwa ce take Shirin fuskanto ni.Tunda nake ban ta'ba rayawa zuciyata auran mutumin nan ba amma lokaci guda kaddara tana nema ta canza tunana.

Mota suka turo da ita aka d'aukemu ni da Babana.
Masaukin da suke mallakinsa ne saboda wasu alamomi dana gani a wurin.
Yawanci ma'aikatan hausawa ne suke yi musu hidima.

Yar uwa wannan littafin na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba. Hakki dai sunansa hakki komai 'kankantarsa mu kiyaye da hakkin junanmu.

Katafaran falo ne mai d'auke da kayan alatu na more rayuwa. Duk wani abu na morewa da jin dadi akwai shi. Sanyi da wani masifaffan kamshin da nakasa tantance turarene ko 'ya'yan itatuwa ya dinga surnanowa hancina. Hotonsa dana mahaifiyarsa gasunan kala kala a manne a falo. Akwai kuma wasu biyu da yake tare da sarkin garin wanda yake a yanzu.
Hakan ya kara tabbatar mini da cewa lallai Yana da Ido a garin saudia domin gidan ya yi kama dana shahararran balaraben da ya ci ya tayar ya tada a kai a kasar.
Guiwata ta kara yin sanyi kawai sai na zubawa sarauta Allah Ido domin lamarin nema yake ya fi karfina.

Cikin mutuminci da karramanci muka gaisa Hajiya Saratu tana ta tsokanata na rasa abinda zan ce mata. Idan ma na yi yun'kurin yin wata maganar sai jikina ya mutu ganin  k'aunar da suke nuna mini basu 'kyamace ni ba.
Hajiyar kuwa bakinta kamar gonar audiga ta sanya an cika gabanmu da abubuwan ci kala kala. Babu abinda ya ba ni sha'awa a ciki. Babanmu dai Ina kallonsa Yana kurbar shayi Yana had'awa da gashashshiyar kaza.

Shigowarsa falon ita ta d'auki hankalinmu gabad'aya. Yana cikin jallabiya fara kal hannunsa rike da wayoyinsa ya zo ya gifta ta kusa da ni kamshinsa ya buge ni. A hankali na bi kafafunsa da kallo farare tas madaidaita ba zaka ce 'kafar namiji ba ce saboda kyau kamar jini zai billo.
Ya d'an tsaya tare da mikawa Babanmu hannu Yana fad'in." Barka da zuwa."
Babanmu ya rike hannunsa sosai yana amsawa.
Ya nemi wuri ya zauna kusa da mahaifiyarsa. Da kyar na daure na danni zuciyata na dube shi.
"Ina yini."
Ya d'an kalle ni babu yabo babu fallasa ya amsa "Lafiya lau ya kike?"

Shiru na yi ban amsa ba. Kawai ma sai na ji kwalla ta ciko idanuna Wannan mutumin ba sa'ana ba ne, bana ra'ayina auran irinsa. Wata'kila ma yana da HIV tunda manemin mata ne.
Hawaye ya fara silalowa a kuncina. Dana san wannan masifar zan riska da na bawa Alhaji Muntari ha'kuri duk tsiya gwara zaman gidansa wallahi.
Ina ji Hajiya tana yi wa Babanmu bayani. Wai ta ji ni a gaban ka'aba ina ta ro'kon miji nagari Wanda zai kula dani ya rike mini yarana. Shine na bata tausayi ta yi sha'awar had'a aurena da d'anta.
Babanmu bai yi wani dogon nazari ba ya amince  har da cewa ko gobe a daura.
Na kasa jurewa kuka ya kwace mini da k'arfi na ce." Hajiya ku gafarce ni, ba fa budurwa ba ce ni, bazawara ce, ina da damar za'bawa kaina abinda nake so, don Allah ku kyaleni ban shirya aure yanzu."

Cikin zafin nama Babanmu ya ce." Dama aure shirya masa ake idan ya zo. Kin je gaban Allah kina rokonsa ya Baki miji nagari ya amshi kukanki ya baki mutumin da kowace mace zata yi Sha'awarsa a matsayin mijin aure, shine zaki butulce masa, wato kin fi so kenan ki cigaba da zaman kanki kina yawo zagade-zagade, kina tallata surarar jikinki a duniya ko Amina, ba zan boye miki ba, salon neman kudin nan naki Yana bata mini rai don dai ba yadda zan yi ne, hanyar abincinmu ne gabad'aya. Ni ne mahaifinki na fi so na bud'e Ido na ganki a d'akin mijinki, idan don mu iyayenki da yaranki kike neman kudin to ki bar shi, Ubangiji ya dubi zuciyarki ya had'a ki da Wanda zai kula dake ya kula damu bakid'aya, muddin da hakkina a kanki Amina ki amince da buk'atar da aka kawo miki."

Cikin mashahurin kukan da yake fitowa daga can cikin cikina. Na ce." Baba ku tambaye shi, ai gashinan a zaune yana da tarin matsaloli, ni na san wasu daga ciki, Shima ya san na sani. Ba zan iya auransa ba domin zan jefa rayuwata a rikici."

Ganin kukan da nake yi ya sanya Hajja kuka itama har tana had'awa da tari. Tana so ta yi  magana tarin ya sarketa kafin wani lokaci jikinta ya fara rikicewa gabad'aya suka rufo a kanta har da Babanmu.....Sai na nami kukan da nake yi na rasa jin sautin nishinta har inda nake zaune. Babanmu ya juyo inda nake Yana fad'in." Zo nan kusa da ita, tana kiranki."
Na tashi da saurin gaske gabana na bugawa! Na tsorata sosai ganin yadda jikinta ya rikice lokaci daya, ina tsoron kada ta mutu sanadin wannan lamari.

Babanmu ya matsa mini na zauna kusa da ita. Sai ya zamana mun sanyata a tsakiya ni dashi ya rike hannunta daya ni ma ina ri'ke daya. Hawaye ya ziraro daga gefan idonta. Sai na sake tsorata tausayinta ya rufe ni. Wane irin so matar nan take yi mini haka. Kuka na fara yi mara sauti ina dan shafa hannunta a hankali a hankali tana so ta yi magana amma ta kasa yi sai dai zirararan hawaye dake fita. A raunane tare da mikawa Allah lamarin nasa bakina daidai kunnanta na ce." Na amince Hajiya na amince, zan zauna dashi in sha Allahu koda kuwa karshen numfashina ne yin haka, na yarda gobe a daura dan Allah kada abinda na fad'a ya dameki, na amince har a cikin zuciyata....✍
*GARKUWAR MATA*
BINTA UMAR ABBALE
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram normal What'sapp group #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#

VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*BOOK2*
*5*
WAIWAYE
Alhaji Tajudden Ibrahimu 'Danbatta kusan zan iya ce muku ya gaji mahafinsa ne wurin gwagwarmaya. Dalili kuwa shine Alhaji Ibrahimu har yau har gobe idan an tashi jero sunayen jajurtattun mutanan da suka yi wa kasarsu hidima dole sunansa ya fito a ciki. A wancen zamanin ya yi da jikinsa kuma ya yi da aljihunsa a matsayinsa na dan kasuwa da yake da kud'i da akidar boko da ilimin addini tare da na zamantakewar rayuwa. Yana daya daga cikin jajurtattun da suka k'watowa kasa 'yancinta. Matarsa daya Halimatssadiya yar uwarsa ce domin da mahafinsa dana nata uwa daya uba daya suke. Mutum ne mai ra'ayi da akida shiyasa ya tsara rayuwarsa yadda yake so kuma Allah Ya amince masa da hakan.
Matarsa daya yaransa biyu har ya koma ga Allah dalilin da ya sanya kenan ko bayan rasuwarsa ba'a yi wata hatsaniya ba. Kaf danginsu suna da rufin asiri kowa yana da nasa babu mai hangen na wani yawancinsu ma sun fi ci da biro 'yan kasuwarsu kalilan ne. Jigo dai a cikin family din shine Alhaji Tajo tunda shine dan kasuwar da ya yi shura a najeria har da wasu kasashen ma.
Tun bayan kammala karatunsa ya fara gwagwarmaya kasuwanci domin shi baya ra'ayina aikin gomanti kamar yadda sauran danginsa suka raja'a. Yi wannan yi wancan, kama wannan saki wancan. Haka ya dinga fadi tashi har Allah kafe shi, ya mallaki kamfanoni akalla sun haura tara tare da gidajen mai sama da biyar bayan manya manyan motocin sufuri wanda suka zama hanyar samun arzikinsa a duniya.
Sai da ya shekara talatin da tara a duniya tukkuna ya fara sha'awar yin aure ba dan bashi da ra'ayi ba sai don sanin cewar ba a hada gudu da susar duwawu!.
Matarsa ta fari auran zumunci suka yi yar kanwar hajiyarsu ce dake zaune a bauchi can dangin mahaifiyarsu su Hajja kenan, a tsarin rayuwarsa yana son mace yar boko kuma yar gayu wadda bata cika jiki da yawa ba, ya fi buk'atar siririya amma mai cikar 'kirji kuma doguwa ko fara ko ba'ka.
yana bala'in son Samira domin itace first love din shi soyayya suka yi sosai kafin ta kai su ga aure. Sai da wata kudira ta Ubangiji ranar da aka daura auransu da daddare ciwon ciki ya murd'eta bata kwana ba rai yayi halinsa.
Tashin hankali wanda ba'a sa masa rana. Ya gigice ya d'imauce! Har ya kusa zautuwa dalilin bala'in son da yake mata kuka kariris ya dinga yi a lokacin gabad'aya ya kasa sarrafa kansa. Haka dai akayi ta koke koke da jimami aka barwa Allah domin shine mai gudanar da komai.

Bayan shekaru hud'u da rasuwar Samira bai kara sha'awar yin wani auran ba, ya cigaba da bunkusa kasuwancinsa duniya na kara suturtashi da

taguwar arziki Allah kuma yana kara sahale masa. Hajja ta zaunar dashi kan batun iyali dalili girma ya fara cimmasa shekara arba'in da hud'u ya kamata ace ya tara yara a halin yanzu. Bai yi jayayya da umarninta ba yace ta nemo masa yarinya mai nagarta sai ayi auran.
Haka kuwa akayi Hajja ta sake binkito masa a dangi amma wannan karon family din Babansu ne Alhaji Ibrahimu.
Ayusha yar yayan mahafinsa ce kusan ma itace yar autar gidansu a mata.
Ya amince duk da bata kwanta masa a rai ba, zai yi ne domin farincikin ta.
Aka gudanar da komai baya kasar yana can India harkokin kasuwancinsa. Amarya ta tare a dankareran gidanta ba ango. Kwana goma da d'aurin auran ya dawo. Wata ijaba da hukunci na Allah dawowarsa da kwana daya don ba wani Abu da ya shiga tsakaninsu dalilin gajiyar da ya kwaso bai tunkareta da wata buk'ata ba. Ayusha ta tashi da matsanancin zazzabi wanda ya dinga sumar da ita tana farfadowa. Babu jinkiri bare bata lokaci aka nufi babban asibiti da ita. Ashe tana da zazzabi typhoid dama yakan tayar mata sa'i da lokaci sai dai wannan karon ya zo da 'karar kwana satinta daya a asibiti rai yayi halinsa.
Babu wanda bai tsorata da wanna lamari ba. Kafin kice kwabo kowa ya fara juya al'amarin ana dangatashi da makaru ko dai shafar aljanu da sauransu. Da yake ya riga ya yi suna a duniya duk yadda akayi ga boye sha'aninsa baya boyuwa sai duniya ta ji. Nan take jaridu da kafafan sadarwa suka samu abin yi. Kowace majiya da irin 'karyar da zata girba. Akwai masu cewa ma aljanar da ta aure shi ta gindaya masa sharad'in bashi ba aure. Wasu kuma suna cewa asharadin dukiya da shahararsa babu aure. Shiyasa duk matar da ya aura zata mutu. Zantuka masu kyau da muni suka dinga dawowa kunnansa. Uffan bai ta'ba cewa ba, har kura ta lafa jama'a suka mance da al'amarin, don ma a lokacin harkokin media basu yi karfi ba wata'kila da har yanzu maganar Bata mutu ba.
Hajja ta ki hakura duk da shi din ya sare da lamarin auran. Ta samu inna Uwani kanwarta ce uwarsu daya ubansu kuma itace mahaifiyar Samira ta je mata da buk'atar a yi masa madadi da Hauwa kanwar Samira ce don itace ma take bin ta a shekaru. Inna Uwani ta dinga zille-zille tana kaucewa, yau ta ce wannan gobe ta ce wancan. Duk lokacin da Hajja za ta tuntubeta da maganar sai ta kawo uzuri. Daga karshe ma sai ta dinga Jin wasu zantuka na tashi a cikin dangi inna Uwani da ita Hauwan suna fad'in haka kawai suna ganin kashi da rana ba za su taka ba. Tunda sun rasa Samira sun bar wa Allah, amma ba zai yiwu ba sai dai ya je can wani wuri ya nema.
Hajja ranta ya yi mummunan baci har sai da ta zubar da hawaye akan kyamar da 'yar uwarta ta nunawa jininta. Daga karshe sai kawai ta ha'kura ta barwa Allah sai dai koyaushe cikin tsananta addu'a take yi a kansa akan Allah Ya magance masa matsalarsa.

Shi ma tun daga lokacin sha'awar aure ta fice masa daga rai domin shima ya tsorata ainun har ya fara zargin kansa yana hasashen kada dai maganar da jama'a suke yi ta zama gaskiya.

Dalilin ciwon mahaifiyarsa kenan Hajja hawan jini mai k'arfi ya kamata. Ashe da sugar a kwance sai shima ya tashi duk a lokacin aka dinga dau'ki ba dadi da ita ana neman rai 'kasa-'kasa har dai Allah Ya sassauta mata aka dawo da ita. Sai dai sa'i da lokaci ciwon yana tashi mussaman idan ta shiga yanayi na b'acin rai da fargaba. Amma da yake macace mai tawakkali bata ta'ba gazgata maganar mutane akan yaronta ba. Ta amince Allah ne yake saukar da ikonsa a kansa, kuma duk wanda ya mutu lokacinsa ne yayi har yanzu bata yarda yaronta yana tare da makaru ko wata aljana ba. Allah ne me yi kuma shi ta mikawa lamarin gabakidaya. Wannan dalilin ne ya sanya take yawan zuwa kasa mai tsarki domin ta yi masa addu'a akan Allah ya kawo karshen matsalarsa. Girma da manyan shekaru sun hau kanta tana so kafin rayuwarta ta kare taga yaransa.
Ganin Amina na ro'kon Allah akan miji nagari a take ta ji a ranta Allah ya kar'bi adduarsu bakidaya dalilin da ya sanya kenan ba ta yi shiru ba ta nemi alfarmar yarinyar wanda ta hangi dacewar auran nasu da samun albarka mai tarin yawa.

Wannan kenan...

Wani irin numfashi take fesarwa idanuwanta a rufe jikinta gabad'aya ya saki.
Gabad'ayanmu muka gigice! Mussaman shi uban gayyar ya tararrayota jikinsa ya rungume yana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ni kam Ina daga zaune amma kafafuwana sai karkarwa suke yi. Sai na nemi kukan da nake yi na rasa tsabar tashin hankali da d'imuwa. Ban san lokacin dana je na rungume kanta a kirjina ba ashe na hada da hannunsa. Ya cire da saurin gaske. Ya tashi da sauri d'akin da ya fito ya shiga Hajiya saratu ta zauna a wurin da ya tashi tana share hawaye. Ganin yadda na d'uka kanta ina yi mata addu'a sai itama ta fara yi. Tana tofa mata kamar yadda nake yi. Hannuna a saman kirjinta ina dan shafawa a hankali a hankali numfashinta ya daidaita. Jikin nata kuma ya daina karkarwa.
Babanmu na gefena a tsaye ya rasa yadda zai yi in banda kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un babu abinda yake yi.

Ya fito yana waya da harshen larabci kimanin minti uku ya gama wayar ya je kusa da 'yar'uwarsa ya tsaya ita dashi duk suka ba ni tausayi ganin yadda suka d'imauce.
Falon ya yi tsit! kowa da irin abinda yake sa'kawa a zuciyarsa.

Wannan littafin dai na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina na, duk kankantar hakki sunansa hakki mu kula sosai!

Kai na shiga rud'u ba k'arami ba. Ni tsorona Allah da Annabi kada ta mutu na zama ina da hannu a ciki. Har likitan ya zo ya gama abinda zai yi bana cikin hankalina.

Na dai tsinci kad'an daga cikin bayanin da yake yi akan tashin ciwon wani labari taji ya firgitata ko dai taga wani tashin hankalin har jinita ya haura ka'ida dole a kiyaye."
Baba ya ce ba zamu tafi ba har sai ta tashi daga bacci ya tabbatar mata da cewa aure kamar an yi shi an gama. Ni ma ban bada goyan bayan tafiyar ba dalili na san hankalina ba zai ta'ba kwanciya ba in ba gani nayi ta tashi ba.
Anan muka kwana sai gefin asuba tukkuna ta motsa.
Da yake ina kusa da ita da sauri na ri'ke hannunta ta fara yun'kurin tashi zaune Hajiya Saratu ta zo ta taimaka mini muka tayar da ita. Ta zuba mini ido tana kallo. Sai na rike hannunta da kyau na ce." Sannu Hajja ya jikin naki?"
Muryata rad'au ta furta." Na ji sauki ina Tajo?"
Da sauri na daga kaina yana can saman wani gado a kwance wata'kila bacci ne ya shammace shi.
Hajiya saratu ta ce ." Gashi can a kwance wata'kila bacci ne ya d'auke shi."
Sai ta girgiza kanta kawai ta tashi tana fad'in." Sallah zan yi." Muka kamata muka kaita bandaki ta kama ruwa ta dauro alwala. Jikinta yayi kwari sosai a tsaye tayi sallarta cikin nutsuwa.
Hankalina ya kwanta sosai ganin yadda Allah ya rufa asiri ciwon bai tsananta ba.
Bayan duk mun gabatar da salla an gaisa da juna. Babanmu ya dubeta yana fad'in." Hajiya maganar nan tana nan in sha Allahu za a daura auran Alhaji Tajo da Amina muddin Hakan shine kwanciyar hankalinki. Yau Juma'a kamar yadda kika buk'ata sai a nemi albarkar ranar. Duka ni da ita mun mikawa Allah lamarin shine yake da iko damu bakidaya."

"Ta d'an dube ni a hankali kafin ta ce." Amina na janye maganata, ba zan sanya ki kiyi abinda ranki baya so ba. Kamar yadda ki ka fad'a kina da za'bi a rayuwarki. Allah Ya za'ba muku abinda yafi alheri gabad'aya. Za mu cigaba da zumunci daku in sha Allahu rabbi."

A lokacin da ta fad'i maganar rasa abin yi nayi duk sai na diririce! Magana nake so na yi amma bakina ya yi nauyi.
Ban ta'ba ganin tsananin fushin Babanmu ba sai a lokacin. Ya rufe ni da fad'a ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba. yana cewa shi ya haife ni ba zai yi mini baki ba, ammafa da wahala na samu miji kamar wannan. Hawaye masu zafi suka dinga gudana a kumatuna. Duk yadda na so na fahimtar dashi halin da ake ciki ba zai gane ba, idonsa ya riga ya rufe da cewa babban mutum zai auri jininsa. Babanmu a sanin da nayi masa bashi da kwadayin abin duniya amma yanzu tashi guda ya aminta da auran mutumin da bai tsananta bincike akan halayensa ba.
Kuka nake sosai na gaza cewa komai Ina dai jin hajjan tana ce masa ya bar maganar haka ai don ba a yi auran ba zumunci ba zai yanke ba.
Da kyar na furta." Hajja ku gafarce ni, akwai 'kudurori da manufofi da uzurirrikana da nake so na cika a rayuwata shine dalilin da ya sanya na k'yamaci aure a yanzu. Ba wai ina 'kin jininki ba ne. Ni ya kamata ku k'yamata amma baku yi ba, wallahi na amince ayi auran nan saboda

farincikinki. Yadda lokaci daya kika nuna mini k'auna ni kaina na san idan na nuna 'kyama ga alherin da kike nufina dashi ban yi miki adalci ba. Na yarda na amince Koda hakan zai zama karshen numfashina kenan." Na rushe da wani irin kuka mai karfi. Sai ta kamo ni ta rungume tsam a jikinta tana kuka take fad'in." In sha Allahu zaku zauna lafiya da juna kuma za a samu zuria mai albarka na gode sosai da wannan karamcin da kika yi mini Allah Ya yi niki albarka. Na gode, na gode na gode sosai."

Abin mamaki da al'ajabi. A ranar aka d'aura auran bayan an idar da sallar Juma'a. Shi kuma uban gayyar wanda tunda ake turka-turkar bai tofa tasa ba kawai dai yana ta bin mu da ido, duk abinda mahaifiyarsa ta ce masa ya yi zai ce mata to. Ganin hakan yasa ni ma na sasauta kyamatar lamarin a gabansu. Idan na cigaba da yin tutsu hakan zai nuna cewa na fi karfin mahaifina kamar yadda mutane suke zargi.
Manyan mutane ne suka halarci d'aurin auran a massalaci bayan an idar da sallar juma'a wanda sarki mai zamani a lokacin shi ya daura auran a massalacin Annabi Muhammadu S.A.W.
Na samu gudumuwa sosai daga wurin abokanansa larabawa da suke hurd'a kudi da gold masu yawa.
Kafin kice kwabo labari ya watsu a duniya gidajan yada labarai jaridu da social media sun samu abin yi. Sahihin gidan jaridar da jama'a suka aminta dashi sune suka fara sanarwa a shafinsu na fecebook.
Alhaji Tajudden Ibrahimu shararran dan'kasuwar nan ya auri 'yar gwagwarmaya kuma 'Yar kasuwar nan Amina Salisu mai-hula. Mahafiyar yaron nan Kamalu wadda a kwanakin baya ta yi dogon rubutu na zagi da 'batanci a kansa ashafinta na fecebook. An d'aura auran ne yau juma'a a madina massalaci Annabi Muhammadu S.a.w inda shahararrun mutane suka samu damar halarta. Amarya ta samu gudumuwa sosai daga hannun abokanan ango. Allah Ya basu zaman lafiya.
Wannan dogon bayanin sun yi shine tare da hotona da nashi a had'e......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram akwai normal What'sapp group #700 ga wad'anda karatu a talgrm yake yi musu wahala hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*

*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*6*
Lamarin da ya janyo hayaniya da kace-na-ce, mussaman a social media kowa na fad'in albarkacin bakinsa. Wasu na ganin Alhaji Tajo alfarma ya yi mini ya aure ni. Wad'anda kuma suka san tarihinsa na baya suna ganin kawai kwanana ne ya k'are tunda har kud'insa suka rude ni na aure shi bayan nasan matsalarsa.
Ni dai tunda aka d'aura auran nake ta zubar da hawaye gabad'aya na rasa a da wane ma'auni zan auna lamarin. Wace irin k'addara ce wannan mai sammatsi. Ina zaune a wani d'aki da yake cikin gidansa domin tun jiya da muka zo ni da Baba Hajjan tace mu zauna kawai kayanmu ma dake can masaukinmu sai turawa akayi aka d'aukosu. Ina jin messages (sakkoni) na ta shigowa wayata ban duba ba dalili na riga na san ba ni da nutsuwar da zan bada amsa abinda dai na yanke a zuciyata shine duk wanda ya tambayi ya akayi hakan ta faru zan ce masa ban sani ba. Shigowar Hajiya Saratu d'akin da kaya a hannunta ya sanya da sauri na goge hawayen kumatuna.
Sai ta girgiza kanta ta karaso wurin da nake tana fad'in." Ki yi hakuri don Allah ki daina wannan kukan Amina. Wallahi tallahi kin ji rantsuwar Muslimi ba zamu cutar dake ba. Duk abinda hajiyarmu ta kaunace shi ya zame mana dole mu 'kaunace shi. Kuma albishirin da zan yi miki shine kin yi miji, ba don Tajo d'an'uwana ne ba nake gaya miki haka, mutum ne da rabin mutum. Zai baki kulawa sosai, kuma zaki samu jin dadin rayuwa dake da yaranki. Ki kwantar da hankalinki, kuma jita-jita na mutane ya daina damunki ki barwa Allah lamarinsa tunda ke kanki idan ki ka yi wa lamarin nan duba na tsanaki za ki san shirin Allah ne."

Murmushi kawai na iya bakina ya yi nauyin da ba zan iya ce mata ba na son d'an'uwanta ba. Gashi kuma ina jin nauyinta domin tana da irin sunan Mamana. Kawai sai na sunkuyar da kaina kasa. Ta ajiye mini kayan da ta shigo dashi tana fad'in." Ki shirya yanzu nan ya kira ni a waya na gaya miki za su shigo tare da abokanansa za a yi hoton tarihi."
Tana gama maganarta ta juya ta fita daga d'akin a gaggauce.
Ledojin na bude dogayen riguna ne manya irin na larabawa da hijabai masu kyawun gaske. Da band'aki a cikin d'akin na shiga na yi wanka na fito na zura d'aya daga cikin dogayen rigunan a jikina. Na d'auki karamin hijabi iya kafad'a nasa. Turare na d'auka akan madubi na fesa a jikina na nemi wuri na zauna zuciya gabad'aya a cunkushe.

Sa'kkonin da aka turo mini ta inbox na fara dubawa. Wanda na yi wa duban tsanaki na Anti Yagana da Sahura. Tambayata suke yi shin labarin da suka ji yana yawo a gari da gaske ne. Kuma ya akayi hakan ta faru.
Na basu amsa da gaske ne. Amma ni ma ban san yadda aka yi ba, kawai su taya ni da addu'a. Idan kuma kwanana ya kare suka kula mini da yarana."
Nasa hannu na goge hawayen da ya shiga zarya a kumatuna wanda ya yi daidai da lokacin da aka turo kofar d'akin a bazata na daga kaina muka yi Ido hudu. Ya mayar da kofar ya rufe ruf. Ya nufo wurin da nake cikin shigar larabawa harda alkyabba irin tasu.

Gabana ya dinga bugawa da k'arfi da k'arfi. Zuciyata tana harbawa kamar zata faso kirjina ta fito.
Daf da ni ya tsaya masifaffen kamshin turaransa ya fara surnanowa hancina.
"Amaryar Tajo." Maganar ta daki kunnena. Hanci na ja ban dago kaina ba balle na kalle shi.

Wannan littafin dai na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini muddin ba ki biyani hakkina ba, mu kula sosai hakki komai kankantarsa sunan hakki.

"Na gode sosai, da wannan sadaukarwar taki, kin daraja mahaifiyata. Kin kar'bi ro'konta, wannan dalilin ya sanya na baki gurbi mai girma a zuciyata. Ba ni da ra'ayin aure a yanzu saboda tarin matsalolina. Amma ba ni da k'wanjin yin turjiya ga umarnin mahaifiyata. Kada ki damu yaranki ki zo tare dasu, ai d'a duka na kowa ne, Allah Ya raya su, ke kuma Allah Ya ba ki hakuri da juriyar zama da ni."

"Ba zan iya zama da mazina ci ba. Ba zaka same ni ba har abada. Aure an d'aura dai amma zai zama na kwangila. Zan zauna a gidanka zan cigaba da hurd'odina na yi hakan ne saboda mahaifiyarka, amma ni ba ni da burun auran irinka, abinda yake cikin zuciyata na fito na gaya maka. Kana da damar auro wata, amma ni kam ba zan iya had'a jiki dakai ba."
Ido cikin Ido na gaya masa haka domin tun yanzu gwara ya san manufata. Haka kawai nake masa kallon mai cutuka a jiki. Domin duk mutumin da yake zina ba zaka raba shi da matsaltsalu ba.

Ya jima yana kallona kafin ya nisa. Ya daga kafadarsa yana fad'in." Ai aure ba abin wasa ba ne, ni ba munafiki ba ne, kuma ba zan fara a kan wannan karamin dalilin ba. Ni ya kamata na kyamace ki saboda mazan da ki ka yi tarayya dasu a baya. Amma har kina da bakin fad'a mini magana. Ki zauna a shirye duk lokacin da na tashi kar'bar sadakina zan turo miki likita ta auna ki. Domin ni har yanzu saurayi ne babu wata mace da na sani."

Wani irin kallo na yi masa a watse na ce." Sai dai a auna mu a tare don wallahi ba zan yarda ka shafa mini 'kanjamau ba."
Sai ya fashe da dariya irin wadda ban ta'ba ganin ya yi ba. Ya nuna kirjinsa da hannu yana cewa." Ni ne mai kanjamau!"
Murgud'a bakina na yi na kawar da kaina gefe.

Ya nisa kafin ya ce." Okey to shikkenan yanzu dai ki tashi muje abokaina suna falo wai sai an yi mana hoton tarihi Ina ce Hajiya Saratu ta gaya miki ko?"

Shiru na yi ban bashi amsa ba, kuma ban tashi ba.
"Kin ji ni ko?" Ya fad'a can kasan makoshinsa. Ban motsa ba.
"Amina."

Ya furta sunana a hankali tare da dora hannunsa a kafada. Na goce tare da mikewa tsaye ina gyara karamin hijabin din wuyana. Kawai na tsince shi yana satar kallon kirjina. Da sauri na dan gicciya gabana na faduwa. Ya miko mini hannunsa.
"Sa hannunki a cikin nawa, ai ko ba ma son juna ba za mu nunawa duniya ba ko?" Yafad'a yana matsowa jikina. Na matsa da saurin gaske. Sai ya gyara fuskarsa babu fara'a. Ya furta." Ba na son sakarcin banza, ko kin shirya ba ni kunya ne a cikin mutane? Duk abinda za ki nuna a yanzu kamar kina gayawa duniya yadda akayi auran nan ne, kin san matsayina a ko'ina, kiris jama'a suke jira su samu abin magana. Yadda nake daure zuciyata kema ki daure zuciyarki a yi lamarin nan cikin girma da mutunci ko nawa kike so zan baki."
Hawaye suka zubo mini Ina kuka na ce." Ni bana buk'atar ko kwabo. kuma don Allah ka ce musu ba ni da lafiya su tafi yadda nake jin ciwo a raina ba zan iya nunawa duniya auran so muka yi ba."

"To na ji, yanzu dai ki yi mini wannan alfarmar kin ji ko, a cikin mutanan da suke falon nan akwai manyan 'kasar nan. Kuma kin san balaraben mutum da kara da karramawa, na amince duk yadda ki ka tsara zaman za a tafi a haka, ni ma ai na san tunda na yi rashin Samira a duniya ai babu wata mace da zata maye mini gurbinta. Amma dai ni dake muna cikin damuwa. Ki b'oye kamar yadda nake b'oyewa.

Nasa hannu ina goge fuskata. Sai ya shiga taya ni, Yana cewa."Mutane da fahimta suke Amina, kin ga kukan da kike ta yi ya janyo idanunki sun kumbura sun yi jawur, ummm, ki yi hakuri haka kin ji ko, ki barwa Allah kamar yadda ni ma na bar masa."
Cikin rararshi yake magana yana ta gyaggayara mini fuskata da tafin hannunsa da yake yake kamshi
Na d'auke hannun da sauri bai ce komai ba ya riko hannuna muka fara tafiya a jere daf da za mu fita ya tsaya yana kallona, ni kuwa sai kawar da kai nake yi. Kawai ba zata na ji saukar hannunsa a tudun kirjina da sunan Yana gyara mini zaman karamin hijabin wuyana.
Da sauri cikin zafin nama na buge hannun. Dan ban san ma na yi hakan ba saboda gigicewar da na yi. Na matsa gefe tare da buga kafata. Murya na rawa na ce." Wai menene hakane?"
Ya dube ni cikin nutsuwa ya furta." Menene kuwa, kawai don na gyara miki hijabi shine za ki bige mini hannu."
Zumbura baki na yi." Ba na so ni gaskiya."
"To, na ji ba zan sake ba, mu je, amma ki saki fuskarki."
Ban ce masa komai ba. Amma na saisaita fuskar tawa. Ya kama hannuna muka fita haka.

Har kasa na zube na gaishesu sun kai su shida kuma kamar yadda ya fad'a manya ne don yawancinsu da masu tsaronsu .
Hajja kam sai murmushi take yi ta yi ado sosai cikin wani leshi bulu da farin mayafi. Babanmu ma cikin sababbin kaya.

Hotona akayi sosai duk Ina kusa da shi, wani ya d'an rungomo ni jikinsa wani kuma ya rike hannuna. Shi ma yana ta walwala ni kuwa sai ya'ke na ke yi na rasa abinda yake yi mini dadi a cikin raina.

Gabad'aya da sadakina da kyautukkunan da na samu Hajiya Saratu ta had'a a kwati ta bawa Babanmu shi kuma ya shigo har d'akin da nake ya kawo mini yana kara yi mini bayani sadakina dubu dari biyu ne duk da kudin garin aka biya. Sannan kuma yana kara gaya mini daga zarar mun koma zan tare. Ni dai ban iya ce masa komai ba kawai na ce to shikkenan Baba. Ya kama hanya ya fita zuciyarsa fes. Hawaye na goge ya zame mani dole na zauna gidan mutumin nan ko don dorewar farincikin da Babanmu ya riski kansa a ciki. Duk yadda Allah ya yi da ni shikkenan

****

Shi ya riga mu yin gaba. Kwana biyu muma muka yi dawafin bankwana muka tattaro kayanmu muka nufo gida. Sai da muka fara sauka a gidan Hajja tukkuna da daddare ta sanya direba ya kaimu gida a bakinta ma ni nake jin ogan baya garin a she a legos ya sauka yana can kuma, wai sun yi waya ya gaya mata ranar juma'a na zauna a shirye zai zo mu tafi can din zan zauna.

Na daure na ce." Hajja dan Allah mu zauna tare nan ba na son yin nesa da gida wallahi. Idan Hakan ma ba zai yiwu ba idan yana da gidaje anan din sai ya ajiye a d'aya daga ciki.
Ta ce." Ni ma hakan na so amma ya ce ya fi so ki bishi can din saboda zamansa ya fi yawa a can amma sa'i da lokaci za ku dinga zuwa. Ko Kuma ni na kawo muku ziyara."
Tunda ta fadi haka sai na ja bakina na yi shiru ban sake magana ba. Ita da Babanmu dai sai tattaunawa suke yi.

Koda Sahura ta zo kawo mini Yusi tunda da zan tafi ita ta d'auke shi. Mu ka zauna muna ta nanata yadda al'amarin ya kasance fadi take ko a mafarki bata ta'ba tsammanin hakan zata faru ba. Ni kam ai tun a saudia na riga na gama mikawa Allah lamarin. Sai dai yadda zuciyata take tsalle da rawa shine abinda ya fi damuna. Sai nake ganin kamar ni ma idan na tare a gidansa mutuwa zan yi. Dalilin da ya sanya kenan na gaza jurewa a ranar da Sahura ta zo bayan ta tafi da daddare na kira wayarsa da yake Hajiya Saratu ta sanya mini a wayata. Yana d'agawa na rushe da kuka ina fad'in." Ni ba zan tare a garin da ba ni da kowa ba. Ka bar ni a gidana na kuntau duk sanda ka yi ra'ayi sai ka zo, idan ma ba za ka zo ba shikkenan."
Kuka nake yi sosai irin wanda na tara a cikina. Ya ce." Ni ba zan bijire maganar iyayena ba, ba kuma za ki gindaya mini son ranki na yi ba, na gaya miki ban shirya takarki yanzu ba, idan ma abinda kike tsoro kenan. Ki yi hakuri ki samarwa Hajjja nutsuwa da kwanciyar hankali, ki kuma dubi irin k'aunar da take miki wanda a tarihi babu wata mace wadda na aura ta nuna mata ko da Samira take 'yar kanwarta bata nuna mata so irin naki ba." Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Duk ina biye miki ne saboda ba na son

damuwarta. Idan ba za ki yi don Allah ba ki yanke adadin kudi ko kadarar da kike buk'ata daga wurina ni zan mallaka miki."
Hanci na ja tare da cewa ." Ni bana buk'atar dukiyarka kawai Ina tsoron yarana su zama marayu gaba da baya. Na yi bincike sosai a kanka an ce aljanna ce ta aureka, kuma ba zata bari ka zauna da mace ba, shiyasa duk macen daka aura sai ta mutu. Bayan haka kuma ni babu tsarin auran namiji d'an duniya a rayuwata."

Cikin b'acin rai ya ce." To ni kuma muddin mahaifiyata tana raye a duniyar nan ba zan yi jayayya da ita ba. Ni kaina ba sonki nake yi ba, saboda ni mutum ne mai tsantsami. Kin yi tarayya da maza biyu har kin haihu kafin ni. Mai zai sanya na takale ki kai tsaye na gaya miki babu wata mu'amular aure da zata ratsa tsakaninmu. Mutuwa kuma ko kin aure ni ko ba ki aure ni ba za ki mutu. Wannan itace maganata dake ta karshe. Zan kuma kira mahaifinki na sanar da shi, duk da shi d'in ma na lura kin fi 'karfinsa. Amma dai shine ya haifeku wata'kila zai iya gaya miki ki ji. Idan na zo ba na son bata lokaci ki zauna cikin shiri."
bai jira na ce wani abuba ya kashe wayarsa....✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram, normal gruop what'sapp kuma #700*
*Hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin

Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*7*
Kuka na ci na koshi domin shine kadai abinda zan yi na samu sau'ki a zuciyata. Tunda aka d'aura aurena da mutumin Alhaji Tajo nake ganin abubuwa iri-iri. A gidanmu da jama'ar gari. Matan babanmu wani irin girma suke ba ni sosai, magana cikin taushi balle Baba Sule kullum sai ya zo gidanmu ya rarrasheni da taushin murya, har yana fad'in na godewa Allah da baiwar da ya yi mini. Domin mata da yawa suna can suna ta neman damar dana samu ba su samu ba.
Can 'bangaran Mamanmu ma lamarin ya yi musu dad'i sosai domin da muka yi waya da anti Yagana a cikin maganganunta ban ji inda ta yi kushe da suka akan mutumin ba. Sai ya zama ni kadai ce nake 'kin auran a zuciyata ina kuma dannewa.

Ya Falmata kuwa magana take yi akan ya za a yi da harkokinmu. Na ce mata ta bari na samu nutsuwa tukkuna. yanzu ma shagunana yara ne suke kula mini dasu. Hamusu dai shine jagora.
Har gida na je na yi Gwaggwo bayanin yadda lamarin ya faru. Ta k'arfafa mini guiwa kan na ha'kura kawai domin daka ganin yadda lamarin ya faru shirin Allah ne saboda a mafarki babu wanda ya ta'ba tunanin babban mutum zai iya aurena, ta ce na yi hakuri na bar mata Yusi zata ri'ke itama ta dan samu me d'ebe mata kewa tunda nesa za mu yi wata'kila kafin a gan mu sai an yara. Ba kunya ba tsoron Allah na fashe mata da kuka tabbacin dai ban yi na'am ba.
Ganin haka ya sanya ta janye kudirinta. Ta ce mini zata fita amma ba zata dade ba. bayan fitarta na yi kwance a rumfarta hawaye na zullumi da tunanin abinda zan fuskanta a gaba yana ziraruwa daga idona. Na ji shigowar sa'ko wayata. Koda na duba sai naga shi ne. Yana fad'in wai duk wani posting dana san na yi a social media kama daga Instagram TikTok fece book na cire. Tsaki na ja na ajiye ba ni kuma da niyyar cirewa domin da za a daura auran ba a yi haka da ni ba. Ba zan daina harkokina ba .
Allah sarki Gwaggwo ashe bakin asibiti taje ta had'o kayan tsumi kawai naga ta dora katuwar tukunya akan wuta. Can ta fito da budurwar kaza da kayan dahuwarta har da ciccibi.
Ta yini tana aiki ta kammala tsaf ta dire mini kwanuka a gabana. tsumim kuma ta samu jarkoki uku ta zuba a ciki tana fad'in duk kwanakin da zai yi ba zai lalace ba.
Da wata ce kai tsaye zan ce mata ba zan ci ba wallahi, amma da yake Gwaggwo ta wuce komai a wurina ban musanta ba, hakan nan na ha'kura na zage na ci kazar data dahu da magani. 08089965176. Ciccibin ne na ce na tafi dashi gida da jarkokin tsumin sai nasha a hankali.

Ina kuka tana yi Yusi ma yana nasa haka muka yi sallama tana ta yi mini addu'oi da samun dawammamen zaman lafiya.

To kaf harkokina na damkasu amana a hannun Hamusu dalili shi na aminta dashi. Usaini ma na san yana da amana, amma dai hankalina yafi kwanciya da Hamusun. Ya yi mini alkawarin kula mini da dukiyata da kuma kawo mini cigaba sannan duk abinda yake tafiya zai dinga sanar da ni.
A daran na kira Sahura a waya mukayi sallama. Misalin tara da rabi sai ga maman Bokola matar data koya mini d'inki ashe ta shigo unguwar da yake ta tashi tsayin shekara uku kenan. kuma babu wanda ya san inda ta koma. Na yi cigiyar lambar wayarta har na gaji. Ta ce mini ta ji labarin wanda na aura ne shine da ta shigo garin ta ce bari ta zo ta yi mini murna.
Na yi godiya sosai mukayi musayar lamba sannan na d'auki kudi masu kauri na bata nace ta kara guziri tunda yanzu a can kudu take da zama wato Benin. Har sai da tayi kuka ganin alherin da nayi mata. Ni kuwa murmushi kawai nake yi ina mamakin kukanta itace silar zamana abinda ban yi tsammani ba. Dubu hamshin din dana bata ai ba zan ta'ba biyanta ba. Muka yi sallama.

Ina idar da sallar asubahi ya kira ni. Da kamar kada na daga wayar na danni zuciyata na dauka. Ba mu yi wata duguwar gaisuwa ba ya fara da ce wa." Kin shirya kayanki ko?"
"Eh." Na bashi amsa a takaice. Ya nisa kafin ya ce ba damuwa ni ma zan sauka misalin sha biyu sai mu bi jirgin yamma."
"To shikkenan." Bai sake wata maganar ba ya kashe wayar. Ni ma na kashe tawa na ajiye a gefe na sa hannu ba bubbugi fillon da Yusi yake a kwance . Ya tashi da sauri yana tambayata tafiya zamu yi. Na ce." Yusi babu salati da addu'ar tashi daga bacci ko."
Sai ya hau motsi da bakinsa. Bayan ya kammala ya dube ni, a raunane Ya furta." Mama mafarki na yi da Yayana  yana biyo ni a bayana." Sai hawaye shaaaa! Suka fara gudana a kumatunsa. Ya cigaba da cewa." Kin ce zamu je makarantar mu duba shi ko Mama, gashi kuma yanzu kin yi aure za mu yi nesa da gari na ji ana cewa Legos da nisa. Ni dai ki barni a hannun Gwaggwo duk lokacin da baba Hamusu za shi duba shi sai ya tafi da ni."
Kuka yake sosai da sosai. Ni kaina daurewa nake yi, kuma a yadda na tsara shine daga na dawo daga umarar nan zan je na duba shi, sai dai kana taka Allah yana nasa.
Ban yadda hawayen da yake kwarmin idona ya zubo ba. Na janyo yaron jikina sosai na rungume cikin taushin murya da rarrashi na ce." Za mu je ne in sha Allahu, ni ma Yayanka yana raina Yusi na gaya maka fa yana can yana karatu yayi hankali zai zama malamin al'kur'ani, ko baka so ya zama abinda duniya za ta yi alfahari dashi."
Cak ya tsayar da kukan da yake yi, Ya dago kansa yana kallona ya ce." Mama da gaske ki ke ko?"
Na gyada kaina tare da gayyato murmushi a saman fuskata nace." I, mana ai ina yi masa addu'a sosai, kuma don na yi aure a nesa dashi zai hana ni na manta dashi ba. Don haka ka kwantar da hankalinka ka ji ko, kai ma ka dinga yi masa addu'a."

To maganganun da na yi sun dan sanyawa yaron nutsuwa. Da kuzari ya tashi ya fita domin dauro alwala. Ni kuma na fara had'a kayana da nasa cikin akwatu. Sai a lokacin hawayen da nake dannewa suka fara zuba. Kasa jurewa na yi kwata kwata domin kaina ya riga ya daukin zafi. Tunaninka iri iri sun dabaibaye ni. Na rasa da wane irin ma'auni zan auna wannan rikitattacen lamarin da ya ritsa da ni a sa'i daya ban shirya ba.
Babanmu ya shigo ya ritsa ni a d'akin. Fad'an da bai ta'ba yi mini ba a duk aure auren da na yi yau shi ya dinga yi mini. Kukana ya tsananta domin sai nake ganin kamar ba a yi mini adalci ba, har zuciyata tana zargin Baban namu akan rintse Ido saboda abin duniya. Shi fa mai kudi duk binciken da za a yi a kansa mai gaskiya ne. Dalilin kudinsa sun shafe masa wata mas'alar. Ba wanda zai fito ya ce yana da aibu saboda sutturar da Allah ya yi masa.
Ni na san yana da matsala tuna kafin aure ya ratsa tsakaninmu ya gwada mini na gani. Duk namijin da yake neman mata rayuwarsa ba zata ta'ba kyau ba. Idan na fito na fad'i haka babu wanda zai yarda da maganata.

Direba ya turo da mota ya d'auke ni. To ko a cikin motar ma kasa daurewa na yi na yane fuskata da mayafin jikina ina goge hawaye da hannuna.
Kwata-kwata babu ajandar aure a tsarina a halin yanzu. To amma kaddara ta gifta wanda ban isa na tsallake taba tunda da 'kafata na taka naje inda take. Wahidun k'har Allah kenan mai juya lamari.

A harabar gidan Hajja muka same shi da jama'a da yawa. Da saurin gaske na kawar da kaina, domin kallo d'aya na yi masa na ji gabana na bugawa. Na ri'ke hannun Yusi da yake ta yun'kurin bud'e motar ya fita. Direban da kansa ya zagayo ya bude mana muka fito. Ya d'auko madaidaiciyar akwatina yana kuma ko'karin kar'bar jakata na hana shi. Da sauri yayi gaba da akwatin. Ni kuma cikin nutsuwa na fara takawa ban yi mamakin yadda jama'ar dake wurin ke risina mini ba. Da yawa sun san ni a hoto da sauran kafafan sadarwa.
Koda na isa wurin da yake sai na dan risina a nutse na furta." Barka da yamma." Ya amsa da "Barka dai." A takaice hankalinsa yana kan wani mutum da yake ta yi masa bayani auran da zai yi wa yaransa kuma bai yi musu kayan gado ba.
Da hanzari na shige don yanayin da ya nuna a fuskarsa kamar bai so na tsaya a wurin ba har na gaishe shi. Jin tsoron abinda zai biyo baya ya sanya na bar wurin da saurin gaske.
Na same su su uku a zaune Hajja da Hajiya Saratu sai wata mai kama da hajjan sak da alama 'yar'uwarta ce.
Hajja ta dinga dariya ganin ni da Yusi fadi take." Amaryar Tajo ta iso fatan alheri a gare ki Amina. Allah Ya albarkaci auranku."
Sosai na yi kokarin sakin fuskata duk domin faranta zuciyar dattijuwar na zube a gabanta da fara'ata na ce." Hajja ina yini ya kufan jiki?"
Ta amsa tana me janyo Yusi cinyarta tana cewa." Kai anan za a bar mini kai ko?"
Yana dariya ya fara gaisheta.
Na juya a tsanake na fara gaishe dattijuwar da take kusa da ita. Babu yabo babu fallasa ta amsa mini Hajiya Saratu ita tun kafin ma na kai ga gaishatan ta gaishe ni duk kuwa da cewa itace gaba da ogan. Hakan ya kara sagar mini da guiwa domin duk inda ake neman karamci da kawaici mutanan sun kai, babu girman kai da d'agawa a cikin sha'aninsu.

"Ayyo! Wannan itace dama, ai ina hasashenta duk da cewa Hauwa ta nuna mini hotonta, na ce ai ba social media nake yi balle na ganeta sai yanzu kuma dana ganta a zahiri  na ganeta ina yawan ganin hotonta akan titina ikon Allah."

Dattijuwar dake kusa da Hajja ce ke wannan maganar tana 'kebe baki.
Sunkuyar da kaina na yi sai na ji Hajjan tana fad'in." Ai 'yar kasuwa ce sosai kuma ta sanu akan harkokinta, ai ni irin wad'andan matan burgeni suke yi muddin  zasu rike mutuncinsu."

Sai kawai ta ce." Hum Hajja kenan, fate fate ake tonawa kawai Allah ya rufa asiri."
Falon ya d'auki shiru lokacin zuciyata ta dinga tsalle kiris nake jira matar ta sake wata magana na kare kaina domin na fahimci wani irin kallo take yi mini na marasa tarbiya.

Ya shigo cikin hanzari Yana fad'in." Wanka kawai zan yi mu tafi na bar uzurirrikana da yawa a can." Sai kuma ya tsaya yana cewa." A a Inna Uwani yaushe ki ka zo?"
"Kwanana biyu a garin nan. Na ji labarin ka yi aure shine na zo yin Allah sanya alheri, ashe wannan itace amaryar?"
Yana 'yar dariya ya ce." Itace inna Uwa, ina Hauwa ba tare kuka zo ba."
Ta kawar da kanta tana cewa" To me Hawwa zata zo ta yi maka Tajo, humm Allah ya Kyauta."

Murmushi ya yi kawai a gaggauce ya shige yana cewa'' Bari na yi wanka na fito.

Ta kasa daurewa sai ta fara fad'in." Duk tsiya dai gwara ta gida, kuma budurwa nutsatsiyar bafulatana. Ai kowane maganarci yana so ya samarwa zuri'arsa uwa ta gari. Babu wayewa ga auran 'yan social media wad'anda suka kwashe kayansu daga gaban ma'aiki."

Hajiya Saratu ta ce." Inna Uwani wace irin magana ce wannan kuma? Babu dadi cin zarafi ga mutumin da bai yi maka komai ba. Wannan auran hukuncin Allah ne. Kuma tun farko mun so ki bashi Hauwa tun kafin ma ya yi aure na biyu ki ka ce ba zaki bashi ba, saboda Salima ta mutu itama kada ta mutu. Har dake fa masu fad'in yana da aljana to me zai sanya kuma bayan Allah ya aurar dashi ga za'binsa ki damu. Yau kusan sati daya da d'aurin auran nan alheri muke ta gani. Don Allah kada ki kawo mana rud'ani."
Sai ta rushe da kuka tana cewa." Saratu fitsara za ki yi mini akan na fad'i gaskiya har kina cewa har da ni a masu yi wa Tajo zagon kasa ko kin manta uwarsa ce ta saki nono taba ni."

Hajja tace "Saratu kyaleta kada na sake jin kin ce komai. Ke kuma Uwani ki tayar mini da ciwona kin ji ko?"
Shiru tayi tana sha'kar hanci tare da sanya gefan d'ankwalinta tana goge hawaye, tana girgiza kanta tana ta kallona. Ni kuma ta kasan idona nake hangenta.
Kusan daskarewa na yi a wurin ganin yadda muraran matar ta nuna zazzafar kiyayyarta a kaina.

Ya fito tsaf cikin manyan kaya. Wurin ya cika da kamshinsa. Ganin inna Uwani na share fuska sai ya ce." Me ya faru ne na ga fuskokinku duk a b'ace.
Hajiya Saratu ta furta." Maganar Hauwa ta taso da ita. Inna Uwani ta so dama ranta ya baci ne kawai."

Ya zuba mata Ido a tsanake ya furta." To idan wannan ce matsalar ki share hawayenki. Bari mu ga abinda Allah zai hukunta  anan gaba idan da rabo sai ayi yadda ki ke so."

"To ai haka ya kama a gaya mini. Ni ban k'yamaci matarka ba Tajo, amma dai ka dawo gida ka yi auran alkunya da fita kunyar jama'a." Ba tare da ya ce mata komai ba ya kalle ni." To zamu tafi yanzu." Ya dubi Hajja da gabad'aya ranta yake a b'ace kan abinda 'yar uwarta ta yi. Ya ce." Za mu tafi Hajja a yi mana addu'a."✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE *
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram akwai normal What'sapp group #700  ga wad'anda karatu a talgrm yake yi musu wahala hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR

jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*6*
Lamarin da ya janyo hayaniya da kace-na-ce, mussaman a social media kowa na fad'in albarkacin bakinsa. Wasu na ganin Alhaji Tajo alfarma ya yi mini ya aure ni. Wad'anda kuma suka san tarihinsa na baya suna ganin kawai kwanana ne ya k'are tunda har kud'insa suka rude ni na aure shi bayan nasan matsalarsa.
Ni dai tunda aka d'aura auran nake ta zubar da hawaye gabad'aya na rasa a da wane ma'auni zan auna lamarin. Wace irin k'addara ce wannan mai sammatsi. Ina zaune a wani d'aki da yake cikin gidansa domin tun jiya da muka zo ni da Baba Hajjan tace mu zauna kawai kayanmu ma dake can masaukinmu sai turawa akayi aka d'aukosu. Ina jin messages (sakkoni) na ta shigowa wayata ban duba ba dalili na riga na san ba ni da nutsuwar da zan bada amsa abinda dai na yanke a zuciyata shine duk wanda ya tambayi ya akayi hakan ta faru zan ce masa ban sani ba. Shigowar Hajiya Saratu d'akin da kaya a hannunta ya sanya da sauri na goge hawayen kumatuna.
Sai ta girgiza kanta ta karaso wurin da nake tana fad'in." Ki yi hakuri don Allah ki daina wannan kukan Amina. Wallahi tallahi kin ji rantsuwar Muslimi ba zamu cutar dake ba. Duk abinda hajiyarmu ta kaunace shi ya zame mana dole mu 'kaunace shi. Kuma albishirin da zan yi miki shine kin yi miji, ba don Tajo d'an'uwana ne ba nake gaya miki haka, mutum ne da rabin mutum. Zai baki kulawa sosai, kuma zaki samu jin dadin rayuwa dake da yaranki. Ki

kwantar da hankalinki, kuma jita-jita na mutane ya daina damunki ki barwa Allah lamarinsa tunda ke kanki idan ki ka yi wa lamarin nan duba na tsanaki za ki san shirin Allah ne."

Murmushi kawai na iya bakina ya yi nauyin da ba zan iya ce mata ba na son d'an'uwanta ba. Gashi kuma ina jin nauyinta domin tana da irin sunan Mamana. Kawai sai na sunkuyar da kaina kasa. Ta ajiye mini kayan da ta shigo dashi tana fad'in." Ki shirya yanzu nan ya kira ni a waya na gaya miki za su shigo tare da abokananansa za a yi hoton tarihi."
Tana gama maganarta ta juya ta fita daga d'akin a gaggauce.
Ledojin na bude dogayen riguna ne manya irin na larabawa da hijabai masu kyawun gaske. Da band'aki a cikin d'akin na shiga na yi wanka na fito na zura d'aya daga cikin dogayen rigunan a jikina. Na d'auki karamin hijabi iya kafad'a nasa. Turare na d'auka akan madubi na fesa a jikina na nemi wuri na zauna zuciya gabad'aya a cunkushe.

Sa'kkonin da aka turo mini ta inbox na fara dubawa. Wanda na yi wa duban tsanaki na Anti Yagana da Sahura. Tambayata suke yi shin labarin da suka ji yana yawo a gari da gaske ne. Kuma ya akayi hakan ta faru.
Na basu amsa da gaske ne. Amma ni ma ban san yadda aka yi ba, kawai su taya ni da addu'a. Idan kuma kwanana ya kare suka kula mini da yarana."
Nasa hannu na goge hawayen da ya shiga zarya a kumatuna wanda ya yi daidai da lokacin da aka turo kofar d'akin a bazata na daga kaina muka yi Ido hudu. Ya mayar da kofar ya rufe ruf. Ya nufo wurin da nake cikin shigar larabawa harda alkyabba irin tasu.
Gabana ya dinga bugawa da k'arfi da k'arfi. Zuciyata tana harbawa kamar zata faso kirjina ta fito.
Daf da ni ya tsaya masifaffen kamshin turaransa ya fara surnanowa hancina.
"Amaryar Tajo." Maganar ta daki kunnena. Hanci na ja ban dago kaina ba balle na kalle shi.

Wannan littafin dai na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini muddin ba ki biyani hakkina ba, mu kula sosai hakki komai kankantarsa sunan hakki.

"Na gode sosai, da wannan sadaukarwar taki, kin daraja mahaifiyata. Kin kar'bi ro'konta, wannan dalilin ya sanya na baki gurbi mai girma a zuciyata. Ba ni da ra'ayin aure a yanzu saboda tarin matsalolina. Amma ba ni da k'wanjin yin turjiya ga umarnin mahaifiyata. Kada ki damu yaranki ki zo tare dasu, ai d'a duka na kowa ne, Allah Ya raya su, ke kuma Allah Ya ba ki hakuri da juriyar zama da ni."

"Ba zan iya zama da mazina ci ba. Ba zaka same ni ba har abada. Aure an d'aura dai amma zai zama na kwangila. Zan zauna a gidanka zan cigaba da hurd'odina na yi hakan ne saboda mahaifiyarka, amma ni ba ni da burun auran irinka, abinda yake cikin zuciyata na fito na gaya maka. Kana da damar auro wata, amma ni kam ba zan iya had'a jiki dakai ba."

Ido cikin Ido na gaya masa haka domin tun yanzu gwara ya san manufata. Haka kawai nake masa kallon mai cutuka a jiki. Domin duk mutumin da yake zina ba zaka raba shi da matsaltsalu ba.

Ya jima yana kallona kafin ya nisa. Ya daga kafadarsa yana fad'in." Ai aure ba abin wasa ba ne, ni ba munafiki ba ne, kuma ba zan fara a kan wannan karamin dalilin ba. Ni ya kamata na kyamace ki saboda mazan da ki ka yi tarayya dasu a baya.  Amma har kina da bakin fad'a mini magana. Ki zauna a shirye duk lokacin da na tashi kar'bar sadakina zan turo miki likita ta auna ki. Domin ni har yanzu saurayi ne babu wata mace da na sani."

Wani irin kallo na yi masa a watse na ce." Sai dai a auna mu a tare don wallahi ba zan yarda ka shafa mini 'kanjamau ba."
Sai ya fashe da dariya irin wadda ban ta'ba ganin ya yi ba. Ya nuna kirjinsa da hannu yana cewa." Ni ne mai kanjamau!"
Murgud'a bakina na yi na kawar da kaina gefe.

Ya nisa kafin ya ce." Okey to shikkenan yanzu dai ki tashi muje abokaina suna falo wai sai an yi mana hoton tarihi Ina ce Hajiya Saratu ta gaya miki ko?"

Shiru na yi ban bashi amsa ba, kuma ban tashi ba.
"Kin ji ni ko?" Ya fad'a can kasan makoshinsa. Ban motsa ba.
"Amina."
Ya furta sunana a hankali tare da dora hannunsa a kafada. Na goce tare da mikewa tsaye ina gyara karamin hijabin din wuyana. Kawai na tsince shi yana satar kallon kirjina. Da sauri na dan gicciya gabana na faduwa. Ya miko mini hannunsa.
"Sa hannunki a cikin nawa, ai ko ba ma son juna ba za mu nunawa duniya ba ko?" Yafad'a yana matsowa jikina. Na matsa da saurin gaske. Sai ya gyara fuskarsa babu fara'a. Ya furta." Ba na son sakarcin banza, ko kin shirya ba ni kunya ne a cikin mutane? Duk abinda za ki nuna a yanzu kamar kina gayawa duniya yadda akayi auran nan ne, kin san matsayina a ko'ina, kiris jama'a suke jira su samu abin magana. Yadda nake daure zuciyata kema ki daure zuciyarki a yi lamarin nan cikin girma da mutunci ko nawa kike so zan baki."
Hawaye suka zubo mini Ina kuka na ce." Ni bana buk'atar ko kwabo. kuma don Allah ka ce musu ba ni da lafiya su tafi yadda nake jin ciwo a raina ba zan iya nunawa duniya auran so muka yi ba."

"To na ji, yanzu dai ki yi mini wannan alfarmar kin ji ko, a cikin mutanan da suke falon nan akwai manyan 'kasar nan. Kuma kin san balaraben mutum da kara da karramawa, na amince duk yadda ki ka tsara zaman za a tafi a haka, ni ma ai na san tunda na yi rashin Samira a duniya ai babu wata mace da zata maye mini gurbinta. Amma dai ni dake muna cikin damuwa. Ki b'oye kamar yadda nake b'oyewa.

Nasa hannu ina goge fuskata. Sai ya shiga taya ni, Yana cewa."Mutane da fahimta suke Amina, kin ga kukan da kike ta yi ya janyo idanunki sun kumbura sun yi jawur, ummm, ki yi hakuri haka kin ji ko, ki barwa Allah kamar yadda ni ma na bar masa."
Cikin rararshi yake magana yana ta gyaggayara mini fuskata da tafin hannunsa da yake yake kamshi
Na d'auke hannun da sauri bai ce komai ba ya riko hannuna muka fara tafiya a jere daf da za mu fita ya tsaya yana kallona, ni kuwa sai kawar da kai nake yi. Kawai ba zata na ji saukar hannunsa a tudun kirjina da sunan Yana gyara mini zaman karamin hijabin wuyana.
Da sauri cikin zafin nama na buge hannun. Dan ban san ma na yi hakan ba saboda gigicewar da na yi. Na matsa gefe tare da buga kafata. Murya na rawa na ce." Wai menene hakane?"
Ya dube ni cikin nutsuwa ya furta." Menene kuwa, kawai don na gyara miki hijabi shine za ki bige mini hannu."
Zumbura baki na yi." Ba na so ni gaskiya."
"To, na ji ba zan sake ba, mu je, amma ki saki fuskarki."
Ban ce masa komai ba. Amma na saisaita fuskar tawa. Ya kama hannuna muka fita haka.

Har kasa na zube na gaishesu sun kai su shida kuma kamar yadda ya fad'a manya ne don  yawancinsu da masu tsaronsu .
Hajja kam sai murmushi take yi ta yi ado sosai cikin wani leshi bulu da farin mayafi. Babanmu ma cikin sababbin kaya.
Hotona akayi sosai duk Ina kusa da shi, wani ya d'an rungomo ni jikinsa wani kuma ya rike hannuna. Shi ma yana ta walwala ni kuwa sai ya'ke na ke yi na rasa abinda yake yi mini dadi a cikin raina.

Gabad'aya da sadakina da kyautukkunan da na samu Hajiya Saratu ta had'a a kwati ta bawa Babanmu shi kuma ya shigo har d'akin da nake  ya kawo mini yana kara yi mini bayani sadakina dubu dari biyu ne duk da kudin garin aka biya.  Sannan kuma yana kara gaya mini daga zarar mun koma zan tare. Ni dai ban iya ce masa komai ba kawai na ce to shikkenan Baba. Ya kama hanya ya fita zuciyarsa fes. Hawaye na goge ya zame mani dole na zauna gidan mutumin nan ko don dorewar farincikin da Babanmu ya riski kansa a ciki. Duk yadda Allah ya yi da ni shikkenan

****
Shi ya riga mu yin gaba. Kwana biyu muma muka yi dawafin bankwana muka tattaro kayanmu muka nufo gida. Sai da muka fara sauka a gidan Hajja tukkuna da daddare ta sanya direba  ya kaimu gida a bakinta ma ni nake jin ogan baya garin a she a legos ya sauka yana can kuma, wai sun yi waya ya gaya mata ranar juma'a na zauna a shirye zai zo mu tafi can din  zan zauna.

Na daure na ce." Hajja dan Allah mu zauna tare nan ba na son yin nesa da gida wallahi. Idan Hakan ma ba zai yiwu ba idan yana da gidaje anan din sai ya ajiye a d'aya daga ciki.
Ta ce." Ni ma hakan na so amma ya ce ya fi so ki bishi can din saboda zamansa ya fi yawa a can amma sa'i da lokaci za ku dinga zuwa. Ko Kuma ni na kawo muku ziyara."
Tunda ta fadi haka sai na ja bakina na yi shiru ban sake magana ba. Ita da Babanmu dai sai tattaunawa suke yi.

Koda Sahura ta zo kawo mini Yusi tunda da zan tafi ita ta d'auke shi. Mu ka zauna muna ta nanata yadda al'amarin ya kasance fadi take ko a mafarki bata ta'ba tsammanin hakan zata faru ba. Ni kam ai tun a saudia na riga na gama mikawa Allah lamarin. Sai dai yadda zuciyata take tsalle da rawa shine abinda ya fi damuna. Sai nake ganin kamar ni ma idan na tare a gidansa mutuwa zan yi. Dalilin da ya sanya kenan na gaza jurewa a ranar da Sahura ta zo bayan ta tafi da daddare na kira wayarsa da yake Hajiya Saratu ta sanya mini a wayata. Yana d'agawa na rushe da kuka ina fad'in." Ni ba zan tare a garin da ba ni da kowa ba. Ka bar ni a gidana na kuntau duk sanda ka yi ra'ayi sai ka zo, idan ma ba za ka zo ba shikkenan."
Kuka nake yi sosai irin wanda na tara a cikina.  Ya ce." Ni ba zan bijire maganar iyayena ba, ba kuma za ki gindaya mini son ranki na yi ba, na gaya miki ban shirya takarki yanzu ba, idan ma abinda kike tsoro kenan. Ki yi hakuri ki samarwa Hajjja nutsuwa da kwanciyar hankali, ki kuma dubi irin k'aunar da take miki wanda a tarihi babu wata mace wadda na aura ta nuna mata ko da  Samira take 'yar kanwarta bata nuna mata so irin naki ba." Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Duk ina biye miki ne saboda ba na son damuwarta. Idan ba za ki yi don Allah ba ki yanke adadin kudi ko kadarar da kike buk'ata daga wurina ni zan mallaka miki."
Hanci na ja tare da cewa ." Ni bana buk'atar dukiyarka kawai Ina tsoron yarana su zama marayu gaba da baya. Na yi bincike sosai a kanka an ce aljanna ce ta aureka, kuma ba zata bari ka zauna da mace ba, shiyasa duk macen daka aura sai ta mutu. Bayan haka kuma ni babu tsarin auran namiji d'an duniya a rayuwata."

Cikin b'acin rai ya ce." To ni kuma muddin mahaifiyata tana raye a duniyar nan ba zan yi jayayya da ita ba. Ni kaina ba sonki nake yi ba, saboda ni mutum ne mai tsantsami. Kin yi tarayya da maza biyu har kin haihu kafin ni. Mai zai sanya na takale ki kai tsaye na gaya miki babu wata mu'amular aure da zata ratsa tsakaninmu. Mutuwa kuma ko kin aure ni ko ba ki aure ni ba za ki mutu. Wannan itace maganata dake ta karshe. Zan kuma kira mahaifinki na sanar da shi, duk da shi d'in ma na lura kin fi 'karfinsa. Amma dai shine ya haifeku wata'kila zai iya gaya miki ki ji. Idan na zo ba na son bata lokaci ki zauna cikin shiri."
bai jira na ce wani abuba ya kashe wayarsa....✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim Opey bank
*8*
"Ta ce addu'a kam koyaushe cikin yin ta nake babu dare babu rana, duk wani abu na gaya maka akan yarinyar nan a daran jiya ba wayo da dubararka ba ne Allah ne ya baka ita, amana ce a wurinka. Ka kula da ita da kyau ko bayan raina ban yarda ka munana mata ba. Wannan shine adduata a gareka Allah Ya yi wa auranku albarka.
Ya amsa da "Amin Amin." Ni kam kasa daurewa na yi dalilin abubuwan da suka cunkushe mini a kirji. Ita wannan matar ban santa ba, wata mu'amula bata ta'ba hadani da ita ba amma tana jifana da mugawayen kalamai. Na rarrafa har kusa da ita na kama hannunta hawaye na kasa tsere a kumatuna na ce.
"Hajja ban san da irin kalamin da zan yi godiya a gare ki ba. Hakika kin nuna mini k'auna ba tare da kin san asali da nasabata ba. Kin so ni a lokacin da dama jama'a ke munana zato a kaina. Hakika Ina yaba kyautayi da kawaici da k'aunar da kike nuna mini. Wannan shine ya tilasta mini kar'bar muradinki ba tare dana shirya yin hakan ba. Yadda ki ka zame mini uwa haka za ki same ni mai biyayya ga umarnin ki Hajja ni 'yar halak ce, kuma ina girmama duk wanda ya kaunace ni tsakani da Allah. In sha Allah zan yi kokarin ganin na yi wa umarninki biyayya, na gode sosai da wannan karamcin naki."
Ta ri'ke hannuna katamau! tana kuka take ce wa." Ni ma ai kin taimake ni Amina, ina ga da ba dan ke ba wata'kila da tattake ni za a yi a wurin nan, ke kika fito da ni har na shaki iska. Sannan na ji ro'ko da magiyar da kike wa Allah akan bukatunki. A lokacin Ubangiji ya kimsa mini kasancewarki mata ga Tajo zai zama alheri. Na san an fi karfin ki ne, amma ki kyautata ha'kuri in sha Allah nan gaba kad'an za ki yi farinciki Ubangiji Allah Ya yi muku albarka. Kuma kamar yadda na fad'a miki zan dinga kawo miki ziyara sa'i da lokaci, Allah Ya ba ku zuria masu albarka."

Ban iya amsawa ba sakamakon kukan da ya ci karfina. Na yunkura na tashi da kyar Hajiya Saratu ta kama hannuna muka kama hanyar fita dama shi Yallabai tuntuni ya fice shi da Yusi.
Koda na shiga motar ban iya dubansa ba. yana zaune Yusi a kusa dashi ya bashi wayarsa yana dannawa. Sai ya zamana mun sa yaron a tsakiya. Hajiya ta Saratu ya zagaya gefan da yake zaune suna magana. Ban ji abinda suke

cewa ba saboda ba na cikin nutsuwata. Sai bayan da motar ta tashi tukkuna ta zagayo tana fad'in Amina a sauka lafiya sai mun zo in sha Allahu. Na daure a hankali na ce." In sha Allahu na gode Mamana.
Sai da muka hau titi sosai na juya a hankali na dubi Yusi da yake ta fama yi masa jagwalgwalo a waya na mika hannu na kar'ba ba tare dana dube shi ba na mik'a masa..." Ka kar'bi wayarka kada ya shigar maka wani wurin."

"Ni na bashi ai." Ya fad'a a takaice! ban ce komai ba, na ajiye wayar saman cinyata. Na juyar da kaina gefe. Yaron ya zuro hannu zai d'auka na juyo da sauri tare da buge hannunsa. Da ido na gargade shi. Lokaci guda ya shiga hankalinsa.

Ya dube ni a tsanake yana cewa." Wayar nan tawa ce ai, kuma ni na bashi ina ruwanki idan ya lalata humm? Na lura kina da saurin hannu, da hantara yaro ba abinda ya yi miki kin buge shi, ba ni wayata."
Na mi'ka masa abarsa kamar yadda ya buk'ata. Sai ya kara mikawa yaron. Shi kuma ya'ki kar'ba yana satar kallona.
Ya dube ni ransa a 'bace." Kin nuna masa akwai wata manufa ko?"
Kallonsa na yi da sauri domin ban yi tsammanin fassarar da zai yi mini kenan ba. Ni na yi hakan ne a ko'karin cigaba da kula da tarbiyar yarona. Don ba zan yi sakaci ta samu tangarda ba dalilin na lura shi din kamar ba mai tsawatarwa ba ne.....
Jikina ya mutu sosai ganin yadda ransa ya 'baci, amma kuma girman kaina ya hana na bashi ha'kuri ko na nuna masa nufina ba haka ba ne.
Kafin mu isa filin jirgin yana ta amsa waya tunda na lura wayoyin nasa kusan uku ne manya biyu da karama daya kuma wadda ya bawa Yusin itace bata da wani amfanin sauran.

Har muka isa Legos babu wata muhimmiyar magana a tsakaninmu. Yusi tuni ya langabe a jikina bacci yake sosai. Muna sauka escort dinshi suka tare mu su uku ne, daya ya d'auki Yusi yasa a kafada sauran kuma suka d'ibi kayanmu zuwa mota.

Na 'dan jima ni kadai a mota kafin ya shigo. Domin muna sauka daga jirgi jama'a suka fara taruwa domin gaisawa dashi. Na dinga hangen yadda yake sakewa da mutane da wasa da dariya har da tafawa idan ta kama. Nan na sake fahimtar cewa shi din mutum ne mai sau'kin sha'ani. Kuma dukiyarsa ba ta sanya masa girman kai da d'agawa ba. Yana rayuwarsa ne daidai da kowa.

Ba zan iya fasalta muku haduwar gidanshi ba. Na san dai ni kaina Allah ya gama yi mini gamnakatar na jin dad'in duniya muddin na samu kwanciyar hankali a cikin wannan gidan Allah ya sallame ni anan duniya sai dai na nemi lahirata. Wallahi tallahi a mafarki ban ta'ba tunanin yin irin wannan auren ba balle na hasaso mini shiga irin wad'annan gidajen da muke ganinsu a

kasashen waje. Sai dai Allah yana zartar da buwayarsa ne a duk lokacin da ya ga dama.

Gidan cike da ma'aikata kowa kuma da aikinsa. Tun a haraba suke ta zuwa gaisuwa  sai da muka shiga ciki tukkuna sannan na dan samu nutsuwa. Na yi kokarin daidaita nutsuwata domin ina tsoron ya fahimci rud'un dana shiga. Na nemi kujera na zauna kafafuna na dan karkarwa. Yusi ya zo ya zauna kusa da ni Ina kallonsa ta gefan Ido yana bin katafaran falon da kallo irin na rashin sabo. Gabad'aya jikinsa ya yi sanyi shi kansa babu kuzarin da ya taho dashi.

A nutse ya nufo wurin da muke yana fad'in." Gidanki ne, za ki iya zabar duk d'akin da ya yi miki a cikin dakunan da suke falon nan. Idan kuma kina sha'awar zama a sama sai ki hau ki duba d'akin da ya yi miki. Ni ma a can nake Sannan da safe idan kin huta zan tara ma'aikatan gidan kaf sai na gabatar musu dake, ina fatan babu matsala."

Ajiyar zuciya na sauke tare da dan duban farcen yatsuna. Na ce." Babu komai, shikkenan Allah Ya kaimu." Sai Ya juya da sassarfa ya fara hawa matattakalar benan da take da wani irin kwalmade kwalmade gashi anyi wa karafunan dake jikin benan wani irin ado da zaiba mai kamar gold sai d'aukar Ido yake yi.
Yusi ya tabo ni yana cewa." Mama kin ga irin benan nan ko, a wani film din indiya na ta'ba ganin irinsa lokacin Umma Sahura ta kunna mana sa'in da kika tafi saudia."
Na dube shi sai kawai dariya ta kwace mini. Na ri'ke hannunsa a hankali na ce." Ni ma haka na taba ganin irinsa a wani film.
Ya ce." Mama gidan nan ya yi kyau wallahi."
Shiru na yi ban ce masa komai ba ina ta nazartar girman falon da yadda aka kawata shi da kujeru da labuleye launi launi.

Wani mutum siriri da shigar masu dafa abinci ya fito daga wata kofa hannunsa da wani 'katon tire na silba da abinci a jere akai. Ya dan risina yana gaisheni, na amsa a takaice. Sai ya wuce sama inda maigidan yake da tiren abincin a hannunsa.
Minti biyar ya sauko da abincin yana kallona yake fad'in." Oga ya ce a shirya muku abinci zai sauko yanzu."
"To.'' kawai na iya cewa na tashi a hankali, hannun Yusi na ri'ke na nufi wata kofa na murd'a ta bude muka shiga.

Hajiya 'kawata kuma 'kanwata ko kuma nace yayata wannan littafi mai suna GUDUN AURE na kudi ne kada ki karanta mini sai kin biya ni hakkina. Kada mu raina hakki komai 'kankantarsa.

Bedroom ne babba wanda yake d'auke da katon gado da kwaba bango guda. Gabad'aya kewaye yake da wasu narka narka labuleye masu beza kasan kafet ne mai laushin gaske. Kofar bandaki kawai na hanga a d'akin sai

can gefe da aka shirya shi da kujeru biyu irin na hutawa da teble a tsakiya. Banda sanyi da kamshi mai dad'i babu abinda d'akin yake yi. Na ajiye handbag dita a nutse na cire mayafin jikina. Na dube Yusi da yake ta ko'karin ciro mini wayata daga cikin jaka. Na ce" Ban san a inda ka saba da wasa da waya ba Yusi tunda ni dai ba baka nake yi ba. Dama ina so na gargad'eka kada ka k'ara yi wa maigidan nan wasa da waya ko baka ya yi."

"Mama shine fa ya ba ni kafin ki fito daga gidan Hajja ya ce na yi game, Umma Sahura itama tana ba mu tata, kuma ba mu ta'ba lalata mata ba."
"Duk da haka dai Yusi wayar Umma Sahura daban da wayarsa, ka kula na gaya maka." A hankali ya ce." To, mama."
Bandakin na nufa kai tsaye komai a na buk'ata akwai, na warware babban towel sabo bayan na gama wanka na daura a jikina. Kana na lulluba wani.
Na fito na same shi ya yi tsuru ga wayar agefensa bai d'auka ba sai ya ba ni tausayi.
Na ce." Kana jin yunwa ko?"
Kai ya daga mini. Na ce to bari na watsa maka ruwa ka wartsake." Sai ya kama dariya yana cewa." Mama ai na iya wanka fa a gidan Umma Sahura da kaina nake yi. Na ce." To muje bandakin na gani, idan naga ka iya shikkenan ni ma na huta.
muka shiga bandakin tare na hada masa ruwa ya fara yana ta cudawa Yana cewa." Ai da zamu taho ma don dai kin hana ni, amma da ni zan yi." Na ce." Ai daga yau kai zaka dinga yin abinka tunda naga ka iya." Na juya na fita daga bandakin Ina cewa." Idan ka gama sai ka dauro wannan towel din dana ajiye maka."
Ina fitowa daga bandakin ya turo kofar d'akin ya shigo ko ya akayi ya san muna ciki oho. Wata'kila kuma mutumin da yake masa abinci ne ya  gaya masa ko kuma motsi ya ji. Hannunsa na janye da akwatin kayanmu. Ni kuma gabad'aya jikina ne ya shika sakamakon rashin kamilalliyar suttura ajikina. Towel ne ya dan sauko kasan gwiwata amma duk sharab'ata a waje take sannan kuma kaina babu dankwali babu sabon kitso.
Na dube shi ta kasan Ido har yayi wanka ya canza kaya marasa nauyi. Ya dan tsaya nesa dani yana ce wa." Amina ga kayanku nan, idan kun kammala sai ku fito mu ci abinci, domin Ina so na fita kafin magriba."

A nutse na ce." To shikkenan. Har ya juya zai fita sai ya kara dawowa ya tsaya kusa da ni. " Kin ga text dina shekaran jiya ko?''
Na dube a hankali na ce." Wane irin text?"

Ya kalli cikin idona sosai ya furta." Na ce duk wani posting da ki ka yi a social media ki goge shine abinda na rubuto miki."
"Me yasa zan goge?" Na fad'a ban shirya ba, domin ni ma ji na yi kawai maganar ta subce ta fito."
"Saboda ba na buk'ata wanda ki ka yi a baya ya isa. Ba zan hana ki nema ba, amma ban yarda da fitar da surar jiki da sunan sana'a ba, ki nemi dukiya ta hanyar da Allah ya halasta."

Cikin nutsuwa na ce." Ai ba zasu ta'ba goguwa ba, tunda na jima da saka su, kuma akwai masu serving da download dole za su yi ta yawo. To ai ni tunda na fara neman dukiyata ta hanyar Allah nake nema ban cud'anya da haram ba."

Ya 'bata fuska yana cewa." Kada ki gaya mini maganar banza mana, ko yaro ki ke so ki mayar da ni ok na ji, Ina ganin za ki yi sanadiyar da zan karbe wayar hannunki tunda na lura ke kina da taurin kai. Na ce bana buk'ata ko an gaya miki aure abin wasa ne."

Ni ma cikin bacin rai na ce."Ai ba ayi haka da ni ba a lokacin da za a yi auran. Hajja ba ta ce zan daina neman kudi ba, asalima a cikinsa aka same ni, to me zai sanya kuma yanzu ka tsiro da wata magana."

"Cewa na yi ki goge duk wasu hotunanki da ki dora a shafukanki na sadarwa ba cewa na yi ki daina sana'a ba, akwai hanyoyi da yawa da za ki juya domin janyo hankali costomars. Babu yarjejeniya a cikin abinda ya shafi addini. Ni ba karamin mutum ba ne, ba kuma zan yarda mutumcina ya zube akan hakan ba, dole duk wasu kusakurai da ki ka yi a baya ki gyara su. Idan kuma kin yi jayayya da umarnina zan sanya gabad'aya rufe duk wasu hanyoyin sadarwarki......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal Whasap Gruop kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su

dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*9*
Na dube shi babu fargaba tare da ni na ce." To ai ba haka ake yi ba, kasan ina da hidima da nauye nauye a kaina, me zai sanya lokaci guda ka zo ka ce zaka rusa mini tsarina na shekaru da yawa, idan an yi mini haka zahiri ba a yi mini adalci ba, tunda babu wanda ya san irin wahalar dana sha kafin na ginu. Ina da yara ina da iyaye da 'yan'uwan da nake taimaka musu to me zai sanya sa'i daya ka zo ka ce ga yadda zan yi."
Ya zuba hannuwansa cikin aljihun faffadan wandon da yake jikinsa ya ce" idan na fahimce ki wato har yanzu kina da burina cigaba da tallata surar

jikinki da zummar kasuwanci ko?" Shiru na yi ban ce masa komai ba. Sai ya cigaba da cewa." Ke ko kunya ba kya ji ko wane titi da hotonki a sa'kale kina yake hak'ori da gantsara jiki meye abin burgewa a ciki. To bari kiji duk titin da aka kawo mini rahoto anga hotonki nasa an cire, hakan ne kuma zai faru harkokin zasu tsaya cak muddin ba ki yi yadda na ce ba."
Yana gama maganarsa ya kama hanya ya fice daga d'akin da b'acin rai.  A daidai lokacin ne kuma Yusi ya fito daga bandaki bayan ya yi wanka.
Cikin takaici na gama shiryawa na zauna duk raina babu dadi, maganganunsa kawai suke ta yi mini yawa a k'wa'kwalwata. Ban yi tsammanin zan samu wata matsala daga wurinsa ba don a tunanina tunda ba auran soyayya muke yi ba,  ba zai shigar mini hurumi ba, to sai gashi tun ban kwana a gidansa ba ya fara kafa mini wasu sharadai. Ai ko na goge komai a shafukana na intranet ban isa na goge wanda yake cikin wayoyin mutane ba. Kuma duk tsiya tarihi ba zai ta'ba mancewa da sunana ba.
Zan goge kamar yadda yake so sai dai dole na nemi wata hanyar domin cigaba da janyo hankalin customers ba zai yiwu na yi wahala tsayin shekara da shekaru ba lokaci guda wani ya rusa mini buri. Ban shigo gidansa da niyyar na ci dukiyarsa ba, ni nafi gane na nemi na kaina kawai yafi rufin asiri a duk lokacin da zan yi wa wani alheri ba ni da matsala sai dai na cire ba tare da na je na yi ro'ko ba.
Gabad'aya cikina cunkushewa ya yi na kasa cin komai don sai bayan isha'i ma muka fita falon da zummar cin abinci. Lokacin tuni shi ya fita sai  wani matashi majiyin karfi da yake ta goge a wurin. Ya gaishe ni. Na amsa a tsanake. Wurin abincin muka nufa nida Yusi, shi kuma mai aikin ya fita da sauri. Da kyar na iya cin loma hud'u shinkafa ce dafaduka wadda ta ji kayan lambu da nama. Ga lemuka nan birjik da yake ni din ba ma'abociyar shan lemo mai gas ba ne ko daya ban bud'e ba ruwa kawai na kurba na d'auki wayata ina dubawa. Shi Kam Yusi ya zage ciki sai cin abincin yake yi hankalinsa a kwance.

To haka muka yi kwanan kadaici da zullumi. Yusi dai bacci ya yi sosai, ni kuwa ban iya baccin arziki ba, domin mafarkai na dinga yi marasa kan gado, gashi muna ta fad'a da maigidan, ina ta kuka, sannan na zo na kama mafarkin Kamalu. Yadda Allah ya nuna mini shi a mafarkin ya kwantar mini da hankali, domin a nutse na ganshi da allo a hannunsa yana rubutu da tawada da alkalami. Da asuba da nayi sallah nayi masa addu'a sosai da sosai na roki Allah Ya shirya mini su gabad'aya. Game da mafarkin da nayi da maigidan muna rigima kuwa, ban kawo komai ba a cikin raina, na dai fi tunanin sa'insar da muka yi jiya ce ta assasa mafarkin.
Da wuri mukayi wanka muka shirya da yake dama koyaushe cikin sabbin dinkuna nake ban da matsalarsu. Na shirya cikin atamfa mai ganye wadda akayi wa dinkin bubu da uban aiki a jiki. Normal na daura dankwali ban yi wata kwalliya ba in banda mai dana shafa. Sai na yi amfani da wata humra da Ya Falmata ta aiko mini da ita.  Innalillahi ai gabad'aya d'akin dumewa yayi da bala'in kamshin humarar mai fizgar hankali. Kad'an na shafa amma jikina ko'ina ya dauka. Ina da bala'in son kamshi shiyasa turare ko nawa ne

bana ganin k'yashin saye. Wannan humrar ma tabbas zan tura kudi a sake kawo mini wata domin ta yi mini dadi sosai....08089965176
Yusi ma ya shirya cikin kananun kaya.  Muka nemi wuri muka zauna ganin yadda ya yi zukudum yasa na mika masa wayata. Ya kuwa kar'ba da sauri yana murmushi. Sai na dan zame na kwanta tare da rufe idona ina tunanin yadda za a yi na je duba Kamalu daga nan. Hakan ba zai yi wu ba dole sai da Hamusu domin shine ya kai shi makarantar tafiyar kuwa dole sai dashi.
Kira ya shigo wayata na bud'e idona tare da tashi zaune na kar'bi wayar daga hannun yaron. Koda na duba sai naga maigidan ne. Na daga tare da daidaita nutsuwata na gaishe shi a tsanake ya amsa yana cewa "Ki fito falo zan yi magana da ku."
Bai bari na amsa ba ya kashe wayarsa. Tsaki naja na dan harari wayar  tare da fad'in." Yusi ta shi muje falo."
Ya sauko daga gadon muka kama hanyar fita.

Yana zaune cikin kayan bacci masu santsi kirjinsa duk a waje. Na yi gaggawar kawar da kaina gefe dan ko da zan gaishe ma ban kalleshi ba. Ina jin ganin  ganin hakan ne ma ya share bai amsa mini ba. Sai ya janyo hannun Yusi yana ko'karin d'ora shi a cinyarsa duk girmansa kuwa. Yaron yana nokewa shi kuwa Fadi yake." Aboki ba magana, mu gaisa mana." Yana ta mika masa hannunsa. Ina kallon Yusi yana sinne kai da murmushi a fuskarsa ya rike hannunsa yana cewa." Barka da asuba Baba." Sai ya amsa da sakkakkiyar fuska don yadda yaron ya kira shi da Baba ya faranta masa rai sosai. Yana cewa." Ya kwanan bak'unta wace makarantar kake so na sanya ka"
Saurin sabo da wayewa irin ta Yusi tana ba ni sha'awa sosai, bashi da gidadanci ko kad'an. Ganin yadda suke ta rahar kamar uba da dan cikinsa sai jikina ya mutu mutuka da gaske. Dole ko na ki ko na so na sassautawa mutumin domin hanyar da ya d'auko mai karya lago ce, duk wanda yake nuna k'auna da kusanci kan abinka tabbas kai yake so, koda yana yin hakan ne da zummar yaudara ya faranta mini rai da wannan Alhaji Muntari ya siye zuciyata har na aminta na aure shi. Haka zalika ma wannan mutumin hanyar da ya d'auko kenan. Jikina ya shika sosai na dinga satar kallonsu ina dan murmushi kamar wadda aka yi wa dole.... Ya dube ni a hankali yana cewa." To ke wace makarantar kike ganin za a kai shi umm?" Sai na fara dibi-dibi domin kwarjinin ya yi mini a lokacin da yake tambayata da kyar na furta." Duk wadda aka kai shi Yallabai,  Allah Ya saka da alheri.''
Ya amsa da "Amin." A takaice kafin ya dan lumshe idonsa ya bud'e su a kaina muryarsa can kasa ya ce." In sha Allahu za a kai shi makaranta mai kyau boko da islamiyya sai ya dora karatunsa a inda ya tsaya Allah Ya bashi sa'a. " Na amsa da "Amin Ya Allah mun gode sosai Allah Ya kara arziki."

Har muka gama karyawa ina ta diri dirin yadda zan gaya masa na goge duk abinda na yi posting din kamar yadda ya buk'ata. Wani kwarjini ya kara a idona sakamakon irin karamcin da ya nuna mini akan yarona. Hankalina ya d'auke wurin tunani na ji maganarsa yana cewa." Mu ga wayarki."

Ban yi jayayya ba na mik'a masa. Ya kar'ba yana dubawa sai ya ce ." Ai ba ki bud'e mini ba."
A hankali na ce." Sunana ne da karamin harafi." Ya yi shiru bai ce komai ba. Yadda yake lallatsa wayar shi ya tabbatar mini da cewa ya bude. Akwai lambobin mutane da dama. Har da maza abokan nan kasuwanci ne, saboda wasu idan sun ga tallan kayanmu sukan kira su ce suna so su sayawa iyalinsu kaya. Sai da ma naga abin yayi yawa ne ya sanya na sayi sabon layi na mussaman domin hakan yana wayar Hamusu yanzu haka, amma dai duk da haka akwai wasu a wayata kuma ban yi tunanin ajiyesu zai kawo mini matsala ba tunda babu abinda yake had'a ni da mutum sai idan ya bukaci wani abun.

"Wanene Hamusu na ga kina yawan waya dashi da sa'kkonin gasu nan da yawa ."
Tambayar da ya jefo mini kenan fuskarsa babu yabo babu fallasa.

Wannan littafin na kudi ne 'yar uwata kàda ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ban ji dadin yadda yake mini bincike a waya ba, amma abinda ya yi mini a yanzu shi ya kautar da b'acin raina na jure ban nuna jin haushina ba na ce." Kanin Babansu Yusi ne."
Ya zubo mini idonsa kuri! yana kallo. Sai na ce." Shine wanda na dam'kawa ragamar kula mini da harkokina tunda gaskiya ba zan boye maka ba mun saba sosai kuma yana da amana, na d'auke shi kamar d'an'uwana na jini."
Shiru yayi bai ce mini komai ba yana dai ta cigaba da duddubar wayar. Kimanin mintina goma kafin ya ce." Kin goge ashe?"
Na dube shi a nutse na furta." E, ni ma naga hakan kamar bai dace ba."
Sai ya miko mini  yana cewa." Idan kina bukatar wani taimako game da harkokin kasuwancinki zan taimaka miki in sha Allahu, amma ki kiyaye sosai, kada ki yi abinda zai zubar mini da mutunci, tunda kin san waye ni abu kad'an sai ya janyo mini magana. Bayan haka ma ina da kishi gaskiyar magana kenan ki kula sosai. Akwai lambobin maza a wayarki ki goge wanda ki ka tabbatar ba muharramanki ba ne. Ba zan hana ki zumunci da yan uwa ba amma ki bi a sannu."
A hankali na ce." In sha Allah."
Ya dan tura kujrar da yake zaune ya tashi kai tsaye hanyar fita daga falon ya nufa sai na tsinci kaina da bin sa da kallo ina ayyana abubuwa masu yawa a kan sa da zaman da za mu yi. A haka dai bashi da wata illa namiji ne sosai. amma idan na tuna yana dan ta'ba harkar neman matan banza sai jikina ya yi sanyi. Zina a yanzu ta zama kamar ado mutane sun mayar da ita karamin alhaki.

Kaf ma'aikatan gidan ya tara su a babban falon kowanne ya gabatar mini da kansa. Shi ma ya gabatar da ni a gare su. Yadda ya dinga nuna musu girma da muhimmancina ya kara girma a idona. Na kuma ji dadin haka sosai, cikin

raina ni ma na yi alkawarin yi masa biyayya daidai gwargwado don ganin yadda ya mayar da kansa ba kowa ba a wurina.
To sai zaman na mu ya zama kadaran kadahan. Babu fad'a. Haka zalika babu gaba, amma ba sakin jiki da juna. Makaranta kuwa kamar yadda ya yi alkawari Yusi idan ya tafi tun safe sai shida na yamma kuma kwana goma kacal da fara zuwansa na fahimci akwai karatu da kula a makarantar domin na kan zauna na duba littafansa aikin gidan kam wani sa'in tare muke yi, idan Ina so na fahimci ganewarsa ne sai na bar shi ya yi shi kadai. Kuma cikin ikon zai yi daidai, idan ma da kuskuran kad'an ne. Haka zalika karatun al'kur'ani domin makarantar kowane bangare ana yi musu.

Ina waya da Hajja sosai don wasu lokotan ma ni ce nake kiranta hakan kuwa yana sanyata farinciki ta dinga tambayata babu matsala idan da akwai na gaya mata. Sai dai kawai na yi murmushi nace mata babu komai ai har mun saba da gidan na gaya mata ma Yusi ya fara zuwa makaranta. Haka zalika ma na kan kira Babanmu mu gaisa dasu Anti Yagana. Sahura kam kusan kullum sai mun gaisa ta Whasap kamar yadda nake gaisawa dasu Hadiza kullum daga zarar na bude data sa'kkonin gaisuwarsu nake cin karo dashi suna  fad'in zasu shirya gabad'ayansu su kawo mini ziyara.
Ina mamakin yadda Hadiza ta yi hankali yanzu, amma na fi tunanin wahalar rayuwa ce ta sauyata. Yadda take mu'amulantata kamar ni ce babba. Su Fatima da Hassana da Usaina kam dama ba ni da matsala dasu ko acan baya muna zumunci daidai gwargwado kuma suna ba ni girmana. Amma yanzu abin ya fi tsananin duba da irin yadda Allah ya canza mini rayuwa shiyasa iyayensu ma haba-haba suke yi da ni.

Na kan fito kullum da safe na zauna a falo kafin maigidan ya sauko duk a kokarina na bashi girma. Kamar yadda bai gayyace ni zuwa dakinsa ba, haka zalika ni ma ban yi yun'kurin nufar hanyar ba, Ina dai jiransa a falo ya sauko mu gaisa. Hakan kuma yakan faranta masa rai a zahiri ina gani a fuskarsa. Tare muke zama mu karya gabad'aya har da Yusi wanda wani irin sabo mai girma ya shiga tsakaninsu. Ya kira shi aboki shima ya kira shi aboki ko Baba kuma ranakun da ba makaranta yana hutu a gida har dakinsa yakan gayyace shi, sai dai su bar ni, ni kad'ai a falo. Idan na gaji na shige naje na kwanta. wani sa'in ma abinci can ake kai musu.

Watan mu a uku a Legos ni da Yusi mun yi wata ki'ba. Wuyana ya kara nitsewa ya bi ya tattara guru guru! Kirjina ya sake bunkasa ga tumbi da ya fara yi mini sallama. 'Dan tsayin da nake gadara dashi ya shanye hankalin idan yayi dubu ya tashi. Idan na kalli mudubi sai na gan ni d'ukul! kumatuna ya yi wani fumm! jikina ya kara nauyi. Shi kam Yusi k'ibar kyau ta yi masa ya zanzare sosai ya zama yaron masu kudi domin sutturu manya maigidan yake saya masa 'kanuna da manya.
Gabad'aya sai na ta'allaka faruwar hakan da cimar dana canza da zama wuri d'aya, tabbas ya zame mini dole kuwa na rage ciye ciye don ma mafi akasarin abincin gidan yana cike da ganyayyaki.....✍

Muje zuwa
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k vip akan telegram. Normal gruop what'sapp kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN✍*

*TALLAH!*
☘☘☘☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*

*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*10*
Shawarar da na yanke a ganina kamar itace maslaha ga rayuwata domin har ga Allah na tsani ki'ba, gashi ba ni da wani tsayi ina ganin idan na yi sake ki'bar ta cimma ni, zan dunkuke ne, ga wani uban tumbi da ya yi mini dirar mikiya ba tare dana fargaba.
Kwanaki kusan hud'u ba na zama wurin cin abinci tare da su. Daga zarar ya sauko mun gaisa zan koma d'akina sai yamma can nake tsakurar abinci kad'an, ba kuma zan sake cin wani ba sai gari ya waye. Bai ta'ba tambayata dalili ba sai yau bayan mun gaisa na koma d'akina hijab din jikina na cire na ajiye dama na yi shiri k'ananun kayane a jikina na d'auko wani mayafina mai tsayi na raba shi gida biyu na 'kulle yayi kamar igiya na fara 'yar tsalle duk a kokarina na motsa jikina tunda ba fita nake yi ba, a raina dai Ina da niyyar neman izininsa akan gym d'insa tunda na lura akwai shi a gidan a wasu lukutan nakan gan shi da kayan motsa jiki. Sosai na ta'karkare ina tsallen igiya don ban ta'ba tunanin zai shigo mini d'aki ba tun bayan shigowar da yayi a washe garin ranar dana tare a gidan, shi kuma Yusi suna gama break yake tafiya makaranta. Kawai na ji an turo kofar d'akin. Na juya da saurin gaske a lokacin gabad'aya na tara zufa duk da Ac din dake cikin dakin. A shirye yake don da alama fita zai yi. Gabad'aya duk sai na dabarbarce. Shi kuma ya tsaya a bakin kofar yana kallona ta cikin gilashin da yake idonsa. Na fara nannad'e abinda yake hannuna. Kafin na ja kafata a hankali na nemi gefen gado na zauna gabana na dan bugawa da kad'an kad'an da nishi irin na tsallen da na yi.

Cikin nutsuwa ya k'araso kusa da ni ya tsaya yana ce wa."Tsallen me kike yi haka har da cire kayan jikinki."

Shiru na yi, na kasa ba shi amsa. Sai ya zauna daf da ni, dan har kafadarmu tana haduwa, abinda bai taba faruwa ba ya d'ora hannunsa a saman cinyata

da take waje domin wandon jikina gajere ne bashi da girma sosai. Lokaci guda tsigar jikina ta tashi, tafin hannunsa d'umi da wani irin taushi kamar ba hannun namiji ba. Cikin wani yanayi na yi saurin janye jikina hannunsa ya fad'i ya sauka daga cinyata.  Sai ya sake matsowa jikina sosai dan kusancin yanzu yafi na farko. Hankalina ya tashi ainun. Na yun'kura da sauri zan tashi ya riko  hannuna da k'arfi ya janyo ni na rikito kansa kawai sai ya sanya hannuwansa gabad'aya ya tallafe ni. Ya sanya ha'barsa a dokin wuyana. Cikin tsananin tashin hankali na fara ko'karin raba kaina dashi amma ban samu nasara ba domin wani irin riko ya yi mini mai tsauri wanda ya sanya lokaci kan'kani ga'bobin jikina suka fara amsawa
Ban san abinda ya gigitashi ba kawai ya dinga bin jikina yana shanshanawa yayin da hannuwansa keta mammatsa mini naman  jikina. Sai na rushe da kuka mai tafe da kururuwa domin har ga Allah gani nake yi kamar Yana ko'karin keta mini mutunci duba da irin yadda lokaci guda babu wata sha'kuwa da ala'ka ta soyayya mai k'arfi a tsakanina dashi amma cikin 'yan sakkoni ya samu jikina yana luguigiutawa har da zura hannunsa cikin rigar mamana.
Na dinga doke hannun ina tunkud'eshi da bugun bayanshi ya'ki sakina ya ma sanya k'afafunsu duk biyun ya kanainaiye ni...Shi kansa hularsa da gilashinsa na gado sun fad'i domin a ki'dime yake baya cikin hayyacinsa. Da kyar da na samu ya cika ni, na tashi da sauri na d'auko hijabina na zura domin na lura ganin tsaraicina a waje shine ya asassa faruwar hakan tunda ai muna had'uwa wuri d'aya tsayin wattanin da nayi a gidan bai taba kwatanta rike mini hannu ba balle har ya rungume ni.

Kuka nake yi sosai gabad'aya na tattare a jikin bango banda so ya fita daga d'akin ba abinda nake yi. Ashe k'arfi ne dashi a haka duk da ba wani jikine dashi sosai ba amma yadda ya rike ni kamar ina  hannun katon gardi. Gabana ya cigaba da bugawa sabili da tuna irin mutsukar da ya dinga yi wa tsokokin jikina.
Kusan mintina goma da faruwar al'amarin ya daidaita nutsuwa domin tunda na 'kwace yake kwance lakadan a gado kamar matacce ido a rufe sa'ilin kuwa da naga ya tashi zaune sai na sake tsorota domin gabad'aya ya zama wata kala fatar goshinsa tabi ta tattara kuma babu wani kuzurin kirki a tare dashi.
Ina kallo ya d'auki hula da gilashinsa ya sanya a idonsa ya zo ya tsaya daf da ni, ta cikin gilashin ya tsira mini ido babu yabo babu fallasa ya furta." Yau ce rana ta farko dana fara rungumar wata 'ya mace har na ji wani yanayi mai wahalar fassaruwa a tattare da ni, ban shigo nan da niyyar yi miki wani abu ba domin a raina na ajiye cewa na aminta da duk irin zaman da kike so ayi zan baki goyon baya. Na shigo ne domin na tambayeki dalilin da ya sanya kika daina zaman break fast tare damu, kuma ina so na tabbatar da shin gaskiya ne maganar da Yusuf ya gaya mini cewa abinci sau daya kike ci a yini wai saboda kada ki yi 'kiba to kuma sai lamarin ya canza domin ganin zahirinki ya tayar mini da sha'awata ta d'a namiji, kuma nan ba da jimawa ba zan yi kokarin ganin na kawar da ita." Ya numfasa kafin ya cigaba da cewa."

Ina ganin babu amfanin horar da kai da yunwa domin zama yadda ake so, ke ai daka ganin ki  jikinki na ki'ba ne duk abinda za ki yi domin guje mata sai ta riske ki, a shawarce kada ki kara yi wa kanki horo da hakan. Akwai abubuwan motsa jiki a gidan nan. Ki ci abinci ki koshi sannan ki dinga motsa jikinki, Ina ganin ko kibar ta riske ki ba zata yi miki muni ba. Sai kuma abu na gaba shine in sha Allah cikin satin nan zan turo likita za a yi miki gwaje-gwaje domin tabbatar da lafiya. Ni ma zan nuna miki result dina don hankalinki ya kwanta na yi gwaje gwaje na tun lokacin aurena da Matata Samira Allah Ya gafarta mata. Ni ba yaro ba ne, haka zalika kema ba yarinya ba ce, kin yi aure a k'alla har sau biyu kin san maza, ba zai yiwu a ce kina zaune a haka babu buk'atar d'a namiji ba. Ko ba ma son juna sai mu zama abokanan d'ebewa juna kewa ko ba haka ba ne?"

'Kokari na yi na dubi tsabar idonsa kamar yadda yake duban nawa na furta." Ni ba wani namiji da yake gabana a halin yanzu, maganar kuma ba ka taba rungumar wata 'ya mace ba ko al'kur'ani zaka dafa ka rantse mini ba zan yarda ba. Shin wai ko ka manta ni ce dai matar nan da ta zo ofis dinka ka kawo mata maganar banza. Idan ka manta ni ban manta ba, ka neman matan banza wannan shine abinda ka nuna mini tun kafin k'addarar aure ta shiga tsakaninmu.
Ai na san ciwon kaina duk da aure-auren da na yi nasan mazan dana aura nutsatstsu ne, cikinsu babu wanda ya ta'ba kawo mini irin maganarka. Don haka ni ban shirya yin wata mu'amula da kai ba a yanzu."

Babu damuwa a tare dashi ya ce." Ba zan rantse miki  don ki yarda da ni ba. Ban ta'ba sanin wata mace ba har yanzu idan kin yarda shikkenan idan kuma ba ki yarda ba mu tafi a haka." Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Lokacin dana bijiro miki da buk'atata a can baya na jarrabaki ne,domin ina neman matar aure na kasa samu dalili duk wata mace da zata tunkaro ni da manufarta. Shigowarki ofis dina kawai na ji a raina bari  na gwadaki sai aka ci sa a kika cinye. Lokacin na ji kin kwanta mini a raina Ina jin zan iya auranki duk da ba kya daya daga cikin jerin matan da nake burin na aura. Ashe Allah ya kaddara hakan dalilin da ya sanya kenan da Hajja ta nuna mini ke ban musanta ba, sai dai Ina ta jinjina mazan da ki ka aura shine kad'ai damuwata yadda nake saurayi nan ni ma ina so na auri budurwa domin na ji yadda ake ji."

Cike da takaici na ce." To ai hanya a bud'e take Malam sai ka auro budurwar bai dami Amina ba, yadda babu tsarin auran mace Irina a tare dakai ni ma babu tsarin auran namiji irinka domin har yanzu ban ji zuciyata tana sonka ba."

Na gaya masa hakan domin shi ma ya ji zafin da nake ji a cikin zuciyata. Bai nuna komai ba ya kara kusanto ni yana fad'in." Shiyasa ai nace mu dinga d'ebewa juna kewa kina da sha'awa ni ma ina da ita, ko babu k'auna a zukatanmu ai akwai muradin wani lamari da Allah ya sallad'a a gangar jiki da

ruhi. Don gaskiya babu ra'ayin yin wani auran a yanzu, kuma ni ba zan iya zuba miki Ido ba bayan na san ke halalina ce, sannan Hajja na can a zaune tana jiran shekara mai zuwa ta d'auki jika, kin ga dole na yi kokarin cika mata burinta."
A sakarce na ce." Ai ni maza biyun sun ta'ba ni har na haihu, to me zaka samu a wurina, ai gwara budurwar tunda kai saurayi ne sai kuje ku gwada budurci da samartaka."

Murmushi ya yi kawai ya dubi agogon da yake daure a tsintsiyar hannunsa na hagu yana cewa." Ni dai na gaya miki cikin ko wane lokaci zan iya takarki don gaskiya ba zan iya jurewa ba.  Domin ina ji a jikina akwai wani abu da ki ke amfani dashi don fizgar hankalina zuwa gare ki, amma in banda haka ni sam mata basa gaba."

Yamutsa fuska na yi tare da kawar da kaina gefe. A raina sai nake ta jin haushin yawan ambaton Samira da yake yi. Ko nauyina baya ji. kuma na gano yana sonta sosai tunda ya fad'a itace first love d'insa. Ya juya ya kama hanyar fita daga d'akin yana furta." Ni na fita ki kula da kanki."

Na ja jiki a sabule na nemi gefan gado na zauna Ina nazarin maganganun da ya yi kafin ya fita. Ban ga alamun wasa a cikin maganarsa ba idan na yi la'akari da yadda lokaci kan'kani ya nuna kwadayinsa a kaina kamar yadda ya fad'a cikin kowane yanayi zai iya zuwar mini da bukatarsa.
Gabad'aya kaina ya kulle a yinin ranar na rasa abinda yake yi mini dadi sai sanda Yusi ya dawo daga makaranta tukkun na dan sake. Tare muka ci abinci muna dan ta'ba Hira hana cewa duk lokacin da aka shirya zuwa duba d'an'uwansa Kamalu zai nemi izini a makaranta koda zata kasance ranar da karatu. Shi dai koyaushe maganar Kamalu idan kana so kaga dariyarsa to yi masa zancen d'an'uwansa. Sai na ce ai ya sha kuruminsa  weekend za mu je ranar da makaranta.
To har karfe tara da wani abu maigidan bai shigo ba, abinda bai taba kasancewa ba kenan. Duk rintsi idan ya fita magariba a gida take yi masa sai dai a wasu lukutan yakan sake fita idan ta kama.
Yusi ya damu da maganarsa karshe dai kawai sai gani na yi ya kira wayarsa da yake shi da kansa ya siya masa waya sabuwa a cewarsa zata dinga taimaka masa wurin karatunsa kuma zata d'ebe masa kewa.
Har suka gama wayar idona yana kan yaron shi ma ya dube ni Yana cewa." Gashin nan akan hanya wai ya sallami wasu baki ne da suka zo masa.
A ta'kaice na ce." To Allah Ya kawo shi lafiya.
Minti goma Sha biyar tsakani ya shigo escort d'insa a baya daya da wayoyinsa a hannu dayan kuma da 'yar jakarsa. Kusa da Yusi ya zauna shi kuma da sauri ya k'ar'bi wayoyin dake hannun escort din nasa suka fita. Falalu babban yaronsa da yake yi masa hidima a dakinsa ya shigo da sauri kai tsaye sama ya wuce ruwan wanka zai had'a masa. Sau daya na dube shi na fahimci sauyawarsa domin ba haka ya fita ba. Cikin nazarin da nake na ji Yusi yana cewa." Baba hannunka  da d'umi sosai fa ko baka da lafiya ne?"

Na dubi yaron sai naga hannuwansu a sarke a wuri d'aya. Yayin da shi kuma yake bud'e idonsa a hankali ya dube shi yana cewa." Lafiya lau na fita da yamma nan na ji alamun zazzabi amma yanzu nan zan kira wayar likitana in sha Allahu."
Cike da kulawa ya ce." Allah Ya baka lafiya baba." Ya amsa yana ko'karin tashi. Na yi kokarin cewa." Sannu Allah Ya sawwa'ke." Ba tare da ya dube ni ba ya amsa ya kama hanyar samansa. Yusi ya tashi ya bi bayansa da wayoyinsa da jakarsa. Tausayinsa ne na ji ya dan tsarga mini a lokacin lallai bashi da lafiya ko ga yanayin tafiyarsa.
Ban yi yun'kurin bin bayansu ba tunda bai ta'ba gayyatata ba, na tashi a sanyaye na nufi d'akina domin yin shirin kwanciya, amma kuma motsi kad'an sai gabana ya fad'i haka kawai ciwon nasa ya tsaya mini a rai ban san menene dalili ba. Ina bandaki ina wanka Yusi ya shigo yana kwala mini kira. Gabana ya yanke ya fad'i sai na kasa daurewa har na fito na amsa da ce wa ." Menene wanka nake yi." Muryarsa na rawa yake cewa." Baba ne yanke jiki ya fadi yanzu nan bayan ya fito daga wanka gashi can ya kasa tashi ya ce jiri ne yake dibarsa. Cikin tsananin tashin hankali na ajiye soson hannuna na watsa ruwa a jikina na dauro towel na fito ban ga Yusi a d'akin ba. Ban tsaya sanya kaya ba na d'auki hijabi na zura a ki'dime na fita.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k vip akan telegram Normal What'sapp group kuma #700hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin

Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*11*
Kofar d'akin a bud'e take na shiga sai na ganshi magashiyan a cinyar Falalu shine wanda yake hidima dashi ta fanni abinci da kula masa da dakinsa. Yusi kuma yana tsugune a saitin kansa ya rike hannunsa. Kafin na kàrasa na dinga nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un.
Na tsinci kaina da kiransa da "Baba" Kamar yadda Yusi ke kiransa. Idonsa a rufe. Na dubi Falalu tare da cewa." Ka kira likitansa mana." Ya ce." Na kira shi yana kan hanya in sha Allah."
Gabana na fad'uwa na dan tsuguna kusa dashi na kama hannunsa na ri'ke sai na ji yana ta karkarwar jiki.
Hawaye suka zubo mini lallai d'an Adam ba a bakin komai yake ba. Na dinga sanya gefan hijabina ina goge hawaye haka kawai tausayinsa nake ji har

cikin zuciyata. Likitansa na zuwa shida Falalu suka cicibe shi suka dora a gado. Sai bayan ya gama duba shi ya sanya masa ruwa ya dube ni a tsanake yana tambayata mussababi. Na ce lafiya lau ya fita kawai ya dawo da zafin jiki sai kuma aka zo aka ce mini jiri ya mamaye shi."
Ya ce." Tension ne kawai da kai kawo da lissafi da kuma rashin samun ishashhen bacci da hutu. Dama wasu masu kudin suna fuskantar irin wannan matsalolin ga lafiyarsu. Kwanakin nan sai tunaninsa ya tsananta shine dalilin da ya sanya jinininsa ya haura in banda haka Yallabai yakan jima bai yi ciwo ba. Idan ya tashi sai a dinga kula sosai. Zama dai mu yi waya da safe in sha Allah, Ubangiji Allah Ya bashi lafiya."
Gabad'aya muka amsa da amin. Ya harhada kayansa ya fita. Falalu ma ya kama hanyar fita yana cewa." Hajiya idan da buk'atar wani abu sai a kira ni."
Ban iya ce masa komai ba saboda tunanin da ya yi mini yawa
Ido na zuba masa ya na kwance sambal a gado bacci yake yi numfashinsa na fita a hankali a hankali lokaci guda kwarmin idonsa ya rufta. Ya ba ni tausayi sosai dalilin da ya sanya ma kenan na kasa matsawa nan da can. Ina zaune a gefensa tunani ya yi mini yawa. Wato mu a wautarmu idan Ubangiji Ya baka kudi baka da wata matsalar rayuwa bayan kuma ba haka abin yake ba an ce ma wasu masu kudin koyaushe cikin fargaba suke ga tarin makiya da mahassada bayan lissafi na rayuwa da yadda za a juya dukiyar ta kara bunkusa. Shi wannan mutumin kaf d'insa abin a tausaya masa ne, a yanzu da nake gefansa a zaune nake yin nazari a kan rayuwarsa. Gashi nan sai kudi da kadarori sanayya da d'aukaka shahara a duniya duk Allah ya yi masa. Amma bashi da magaji ma'ana yaran da ko bayan ya rasu zasu gaje shi. A k'alla yanzu shekarunsa sun haura arba'in da biyar wanda a iya sanina idan talaka ne a matakin shekarunsa muddin ya yi auran wuri ya aurar da 'ya mace idan da ita ya fara. yanzu ne na gane dalilin da ya sanya ya d'auki son duniya ya dora akan Yusi ko bai fad'a ba akwai wani ciwo da yake d'ankare a zuciyarsa. Gani dai kusan wata uku a gidansa zazzabi kwana daya ban ta'ba yi ba sai ma kibar da nake shigarwa wannan kadai ya isa ya tabbatarwa da jama'a cewa babu mahalu'kin da yake mutuwa sai kwanansa ya kare. Ni kaina da farko na tsorata amma yadda iyaye da 'yan uwa suke kara mini kwarin guiwa akan tawakkali da yarda da kaddara shine dalilin da ya sanya na barwa Allah ikonsa tunda ko na zauna da Alhaji Tajo ko ban zauna dashi ba idan kwanana ya kare dole na mutu. Hakika ya bani tausayi sosai ta wannan gefen domin haihuwa rahama ce kuma baiwa ce, kowane dan Adan zai so ya bar magaji bayan babu shi a duniya

Na daga kaina can na hangi Yusi kan sofa ya bingire bacci yake yi sosai. Ni kam gabad'aya idona ya soye nazari da lissafin rayuwa ya dabaibaye ni.
Gefen asuba bacci ya shammace ni, na bingire a gefansa ba tare da na san haka ba. Sai ji na yi Yana dan ta'ba hannuna da kiran sunana.
A firgice na tashi zaune da sauri shi ma ya tashi yana ri'ke ni." Menene salati ake yi idan an tashi daga bacci." yafad'a cikin taushin murya.
Na sauke ajiyar zuciya ina dubansa a hankali na ce." Ya jikin naka?"
"Alhamdulillahi Ya furta cikin nutsuwa.

Na ce." Allah Ya kara afuwa.

Ya dubi gefan da Yusi yake kwance yana cewa." Anan kuka kwana ke da Yusuf?"
Sunkuyar da kaina na yi a nutse na ce." E, jiyan ne jikin naka ya rikice sosai baka ma san wanda yake kanka ba."

Ya furta." Shine ki ka ji tausayi na ki ka kwana kusa da ni?"
Shiru na yi ban iya bashi amsa ba. Ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Na gode my wife Allah Ya yi mini albarka." Daga hakan sai ya sauka daga gadon ya nufi bandaki. Na janye idona daga hanyar da ya bi, jikina duk a salube na tashi Yusi domin ya yi shirin massalaci. Ya ce zai je tare da Baba. Ban matsa masa ba, na kyale shi a d'akin ni na kama hanya na fita da tunaninka masu yawa a tare da ni.

Ni a jikina nake jin canzawar yanayi game da mutumin nan. Wani yanayi ne wanda na kasa tantance shin tausayinsa nake yi ko kuma sonsa nake yi ni dai ban sani ba amma ina jinsa a raina, ina kuma jin mugun tausayinsa yadda yake mu'amulantata cikin sau'kin kai hakan yana k'ara karya lago na. Uwa uba k'aunar yarona da yake yi tamkar shine ya haife shi.
Ko yanzu da nake wanka Allah-Allah nake na gama na shirya na koma d'akina domin sanin halin da yake ciki, ni kaina mamakin lamarin nake tsakanin jiya da yau mutumin ya tsaya mini a zuciya.

Cikin doguwar riga mai adon duwatsu na shirya a jikina hankalina na sake komawa d'akin nasa. Sai na tarar dashi a zaune har ya yi wanka yana cikin kananun kaya singiliti da boxar wasu wuraran na jikinsa duk a bayyane. Falalu yana fifita masa shayi shi kuma hankalinsa na kan wayarsa shigowata ta d'auki hankalinsu gabad'aya. Ni Kam jikina ya yi sanyi ganinsa a haka, sai na dinga jin nauyin had'a Ido dashi, duk da ba yanzu na saba ganin namiji da irin shigar jikinsa ba, amma dai shi din kwarjini yake yi mini.
Na ji shi yana cewa da Falalun ya je kawai tunda na shigo. Ya zo ya gifta ni yana gaishe ni na amsa cikin nutsuwa. Ya bude d'akin ya fice, cikin sanyin jiki na kàrasa kusa dashi na dan zauna kan kujerar dake fuskantarsa ina gaishe shi da tambayar jikinsa, ya amsa hankalinsa gabad'aya a kaina. Kallona yake yi sosai wanda ya sanya jikina kara mutuwa. Saukar numfashinsa na ji a hankali ya furta." Yusuf ya tafi makaranta ko?"
Na dube shi ni ma cikin kulawa na ce." Ai kai zan tambaya Yallabai." Sai ya yi murmushi yana cewa." Ai sai da na rarrashe shi tukkun ya tafi ya shirya wai saboda Baba bashi da lafiya ba zai je ba zai zauna ya kula da ni."
Murmushi na yi tare da cewa." Yusi kenan, na jima ban ga mutumin da ya saki jiki dashi kamarka ba."
Murmushi ya yi bai ce komai ba, tsayin minti goma d'akin ya yi shiru sai saukar numfashinmu a hankali na ji maganarsa yana cewa." Ina son Yusuf sosai Ina ji kamar ni na haife shi, Amina ni ma za ki yi mini alfarmar haihuwa ko?"

Yadda ya yi maganar kowaye kai dole ya baka tausayi. Na ce." Ai Allah ne yake bayarwa ranka ya dad'e, kuma indai muna tare Yusuf naka ne, ai ban isa na raba wannan k'aunar ba."

"Na aminta da hakan my wife ni yaushe za ki ba ni nawa?" Ya furta cikin kyakykyawan lafazi. shiru na yi ban iya bashi amsa ba.
Ya nisa kafin ya sake cewa." Kin san ciwon nan nawa har da fargabar yadda zan tunkareki da buk'atata domin na lura da gaske bakya 'kaunata. To kin ga wannan lamarin yana buk'atar soyayya. Da gaske haihuwa nake so wallahi."
A hankali na dube shi tare da cewa." Ka daina cewa ba na k'aunarka don Allah."
Ya ce." To, na daina cewa, amma idan da gaske kina kaunata ki watsar da makamanki kamar yadda na watsar da nawa makaman mu yi rayuwar aure domin zama cikakkun ma'aurata. Sannan ki taso ki zo nan kusa da ni."
Cikin 'yar shagwaba wadda ma ban san ina yi ba na ce.'' Ba ka ce sai an auna ni ba, ni ba zan iya kusantar inda kake ba yanzu saboda kada na shafa maka ciwo."

Ya yi mini wani irin kàllo wanda na kasa gane na menene cikin taushin harshe ya furta. Ni da kike cewa mai kanjamau fa! Ni fa babu wata mace dana sani Amina. Amma kefa maza biyu ni ne ai abin tausayi, kuma dole na ji wa kaina haushi.
Ban iya ce masa komai ba. Ya ce." To, tunda kin ki zuwa ni bari na zo." Ya ajiye wayar hannunsa ya nufo wurin da nake zaune.
Hannun kujarar ya zauna. K'amshin turaransa ya buge ni. Ni dai Ina masifar son kamshinsa ba tun yau ba. A rikice ya riko kafadata yana ko'karin rungume ni ya ce." Ina son wannan 'kamshin na jikinki Amina. Za ki mallaka mini kanki ko?"
A tsorace nake don ban yi tsammanin cewa daga ya zo zai rungume ni ba, bayan haka ma sai hari yake kaiwa k'irjina wanda na fahimci tunda na zauna a d'akin hankalinsa yana kai. Na cire hannunsa da yake ta mammatsa mini jiki a sarke na furta." Baka da lafiya fa Baba sannan ga tea dinka can zai yi sanyi."
Idonsa a lumshe ya kwanto gabad'aya a jikina ya sakar mini nauyinsa yana nishi wanda ya yi masifar daga mini hankali lokaci guda na ji yanayina ya fara canzawa. Wani masifaffan shau'ki na shiga wanda tunda uwata ta haifo ni ban ta'ba jin irin yanayin ba. Ban san yadda aka yi ba kawai na tsinci kaina da tallafar kansa na matse tsam! a kirjina.  Yayin da yake yin nishin ni ma shi din nake yi. Lamarin da ya kara dagula mana lissafi gabad'aya domin yadda na yi masa ya k'ara kidimashi ainun! Ya sake rikicewa Yana ko'karin saka bakinsa cikin nawa. Ni da shi din gabad'aya muka kasa sarrafuwa domin kamar wad'anda aka haifa tare muka zama ita kanta kujerar da muke kai sai da ta jiki karshe ma rigib mukayi a kasan kafet wanda hakan ya zamo silar rabuwar gangar jikinkinmu  tare da dawowa hayyacinmu a lokaci daya.

Bayan rabuwar gangar jikinmu sai ya tsira mini idanuwansa wanda babu alamun risina ko kunya a cikinsu. Ni kuma sai hakan ya kara jefe ni cikin jin kunya da nauyi har nake zargin kaina da bashi kwarin guiwa har ya aikata abinda ransa yake so. A ganina da tun farko na nuna ban yarda ba, ba zai samu sararin yin abinda ya yi ba. D'ankwalin abayata da ya sum'bule ya fadi a kasan wurin na d'auka na d'ora a kaina tare da dan gyara shi yadda zai rufe tudun kirjina, na tashi guiwa a sabule na kama hanyar fita kamar na rushe da kuka haka nake ji a cikin raina....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k vip akan telegram Normal What'sapp group kuma #700hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran

gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*11*
Kofar d'akin a bud'e take na shiga sai na ganshi magashiyan a cinyar Falalu shine wanda yake hidima dashi ta fanni abinci da kula masa da dakinsa. Yusi kuma yana tsugune a saitin kansa ya rike hannunsa. Kafin na kàrasa na dinga nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un.
Na tsinci kaina da kiransa da "Baba" Kamar yadda Yusi ke kiransa. Idonsa a rufe. Na dubi Falalu tare da cewa." Ka kira likitansa mana." Ya ce." Na kira shi yana kan hanya in sha Allah."
Gabana na fad'uwa na dan tsuguna kusa dashi na kama hannunsa na ri'ke sai na ji yana ta karkarwar jiki.
Hawaye suka zubo mini lallai d'an Adam ba a bakin komai yake ba. Na dinga sanya gefan hijabina ina goge hawaye haka kawai tausayinsa nake ji har cikin zuciyata. Likitansa na zuwa shida Falalu suka cicibe shi suka dora a gado. Sai bayan ya gama duba shi ya sanya masa ruwa ya dube ni a tsanake yana tambayata mussababi. Na ce lafiya lau ya fita kawai ya dawo da zafin jiki sai kuma aka zo aka ce mini jiri ya mamaye shi."
Ya ce." Tension ne kawai da kai kawo da lissafi da kuma rashin samun ishashhen bacci da hutu. Dama wasu masu kudin suna fuskantar irin wannan matsalolin ga lafiyarsu. Kwanakin nan sai tunaninsa ya tsananta shine dalilin da ya sanya jinininsa ya haura in banda haka Yallabai yakan jima bai yi ciwo ba. Idan ya tashi sai a dinga kula sosai. Zama dai mu yi waya da safe in sha Allah, Ubangiji Allah Ya bashi lafiya."

Gabad'aya muka amsa da amin. Ya harhada kayansa ya fita. Falalu ma ya kama hanyar fita yana cewa." Hajiya idan da buk'atar wani abu sai a kira ni." Ban iya ce masa komai ba saboda tunanin da ya yi mini yawa

Ido na zuba masa ya na kwance sambal a gado bacci yake yi numfashinsa na fita a hankali a hankali lokaci guda kwarmin idonsa ya rufta. Ya ba ni tausayi sosai dalilin da ya sanya ma kenan na kasa matsawa nan da can. Ina zaune a gefensa tunani ya yi mini yawa. Wato mu a wautarmu idan Ubangiji Ya baka kudi baka da wata matsalar rayuwa bayan kuma ba haka abin yake ba an ce ma wasu masu kudin koyaushe cikin fargaba suke ga tarin makiya da mahassada bayan lissafi na rayuwa da yadda za a juya dukiyar ta kara bunkusa. Shi wannan mutumin kaf d'insa abin a tausaya masa ne, a yanzu da nake gefansa a zaune nake yin nazari a kan rayuwarsa. Gashi nan sai kudi da kadarori sanayya da d'aukaka shahara a duniya duk Allah ya yi masa. Amma bashi da magaji ma'ana yaran da ko bayan ya rasu zasu gaje shi. A k'alla yanzu shekarunsa sun haura arba'in da biyar wanda a iya sanina idan talaka ne a matakin shekarunsa muddin ya yi auran wuri ya aurar da 'ya mace idan da ita ya fara. yanzu ne na gane dalilin da ya sanya ya d'auki son duniya ya dora akan Yusi ko bai fad'a ba akwai wani ciwo da yake d'ankare a zuciyarsa. Gani dai kusan wata uku a gidansa zazzabi kwana daya ban ta'ba yi ba sai ma kibar da nake shigarwa wannan kadai ya isa ya tabbatarwa da jama'a cewa babu mahalu'kin da yake mutuwa sai kwanansa ya kare. Ni kaina da farko na tsorata amma yadda iyaye da 'yan uwa suke kara mini kwarin guiwa akan tawakkali da yarda da kaddara shine dalilin da ya sanya na barwa Allah ikonsa tunda ko na zauna da Alhaji Tajo ko ban zauna dashi ba idan kwanana ya kare dole na mutu. Hakika ya bani tausayi sosai ta wannan gefen domin haihuwa rahama ce kuma baiwa ce, kowane dan Adan zai so ya bar magaji bayan babu shi a duniya

Na daga kaina can na hangi Yusi kan sofa ya bingire bacci yake yi sosai. Ni kam gabad'aya idona ya soye nazari da lissafin rayuwa ya dabaibaye ni.
Gefen asuba bacci ya shammace ni, na bingire a gefansa ba tare da na san haka ba. Sai ji na yi Yana dan ta'ba hannuna da kiran sunana.
A firgice na tashi zaune da sauri shi ma ya tashi yana ri'ke ni." Menene salati ake yi idan an tashi daga bacci." yafad'a cikin taushin murya.
Na sauke ajiyar zuciya ina dubansa a hankali na ce." Ya jikin naka?"
"Alhamdulillahi Ya furta cikin nutsuwa.
Na ce." Allah Ya kara afuwa.

Ya dubi gefan da Yusi yake kwance yana cewa." Anan kuka kwana ke da Yusuf?"
Sunkuyar da kaina na yi a nutse na ce." E, jiyan ne jikin naka ya rikice sosai baka ma san wanda yake kanka ba."

Ya furta." Shine ki ka ji tausayi na ki ka kwana kusa da ni?"
Shiru na yi ban iya bashi amsa ba. Ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Na gode my wife Allah Ya yi mini albarka." Daga hakan sai ya sauka daga

gadon ya nufi bandaki. Na janye idona daga hanyar da ya bi, jikina duk a salube na tashi Yusi domin ya yi shirin massalaci. Ya ce zai je tare da Baba. Ban matsa masa ba, na kyale shi a d'akin ni na kama hanya na fita da tunaninka masu yawa a tare da ni.

Ni a jikina nake jin canzawar yanayi game da mutumin nan. Wani yanayi ne wanda na kasa tantance shin tausayinsa nake yi ko kuma sonsa nake yi ni dai ban sani ba amma ina jinsa a raina, ina kuma jin mugun tausayinsa yadda yake mu'amulantata cikin sau'kin kai hakan yana k'ara karya lago na. Uwa uba k'aunar yarona da yake yi tamkar shine ya haife shi.
Ko yanzu da nake wanka Allah-Allah nake na gama na shirya na koma d'akina domin sanin halin da yake ciki, ni kaina mamakin lamarin nake tsakanin jiya da yau mutumin ya tsaya mini a zuciya.

Cikin doguwar riga mai adon duwatsu na shirya a jikina hankalina na sake komawa d'akin nasa. Sai na tarar dashi a zaune har ya yi wanka yana cikin kananun kaya singiliti da boxar wasu wuraran na jikinsa duk a bayyane. Falalu yana fifita masa shayi shi kuma hankalinsa na kan wayarsa shigowata ta d'auki hankalinsu gabad'aya. Ni Kam jikina ya yi sanyi ganinsa a haka, sai na dinga jin nauyin had'a Ido dashi, duk da ba yanzu na saba ganin namiji da irin shigar jikinsa ba, amma dai shi din kwarjini yake yi mini.
Na ji shi yana cewa da Falalun ya je kawai tunda na shigo. Ya zo ya gifta ni yana gaishe ni na amsa cikin nutsuwa. Ya bude d'akin ya fice, cikin sanyin jiki na kàrasa kusa dashi na dan zauna kan kujerar dake fuskantarsa ina gaishe shi da tambayar jikinsa, ya amsa hankalinsa gabad'aya a kaina. Kallona yake yi sosai wanda ya sanya jikina kara mutuwa. Saukar numfashinsa na ji a hankali ya furta." Yusuf ya tafi makaranta ko?"
Na dube shi ni ma cikin kulawa na ce." Ai kai zan tambaya Yallabai." Sai ya yi murmushi yana cewa." Ai sai da na rarrashe shi tukkun ya tafi ya shirya wai saboda Baba bashi da lafiya ba zai je ba zai zauna ya kula da ni."
Murmushi na yi tare da cewa." Yusi kenan, na jima ban ga mutumin da ya saki jiki dashi kamarka ba."
Murmushi ya yi bai ce komai ba, tsayin minti goma d'akin ya yi shiru sai saukar numfashinmu a hankali na ji maganarsa yana cewa." Ina son Yusuf sosai Ina ji kamar ni na haife shi, Amina ni ma za ki yi mini alfarmar haihuwa ko?"

Yadda ya yi maganar kowaye kai dole ya baka tausayi. Na ce." Ai Allah ne yake bayarwa ranka ya dad'e, kuma indai muna tare Yusuf naka ne, ai ban isa na raba wannan k'aunar ba."

"Na aminta da hakan my wife ni yaushe za ki ba ni nawa?" Ya furta cikin kyakykyawan lafazi. shiru na yi ban iya bashi amsa ba.
Ya nisa kafin ya sake cewa." Kin san ciwon nan nawa har da fargabar yadda zan tunkareki da buk'atata domin na lura da gaske bakya 'kaunata. To kin ga wannan lamarin yana buk'atar soyayya. Da gaske haihuwa nake so wallahi."

A hankali na dube shi tare da cewa." Ka daina cewa ba na k'aunarka don Allah."
Ya ce." To, na daina cewa, amma idan da gaske kina kaunata ki watsar da makamanki kamar yadda na watsar da nawa makaman mu yi rayuwar aure domin zama cikakkun ma'aurata. Sannan ki taso ki zo nan kusa da ni."
Cikin 'yar shagwaba wadda ma ban san ina yi ba na ce.'' Ba ka ce sai an auna ni ba, ni ba zan iya kusantar inda kake ba yanzu saboda kada na shafa maka ciwo."

Ya yi mini wani irin kàllo wanda na kasa gane na menene cikin taushin harshe ya furta. Ni da kike cewa mai kanjamau fa! Ni fa babu wata mace dana sani Amina. Amma kefa maza biyu ni ne ai abin tausayi, kuma dole na ji wa kaina haushi.
Ban iya ce masa komai ba. Ya ce." To, tunda kin ki zuwa ni bari na zo." Ya ajiye wayar hannunsa ya nufo wurin da nake zaune.
Hannun kujarar ya zauna. K'amshin turaransa ya buge ni. Ni dai Ina masifar son kamshinsa ba tun yau ba. A rikice ya riko kafadata yana ko'karin rungume ni ya ce." Ina son wannan 'kamshin na jikinki Amina. Za ki mallaka mini kanki ko?"
A tsorace nake don ban yi tsammanin cewa daga ya zo zai rungume ni ba, bayan haka ma sai hari yake kaiwa k'irjina wanda na fahimci tunda na zauna a d'akin hankalinsa yana kai. Na cire hannunsa da yake ta mammatsa mini jiki a sarke na furta." Baka da lafiya fa Baba sannan ga tea dinka can zai yi sanyi."
Idonsa a lumshe ya kwanto gabad'aya a jikina ya sakar mini nauyinsa yana nishi wanda ya yi masifar daga mini hankali lokaci guda na ji yanayina ya fara canzawa. Wani masifaffan shau'ki na shiga wanda tunda uwata ta haifo ni ban ta'ba jin irin yanayin ba. Ban san yadda aka yi ba kawai na tsinci kaina da tallafar kansa na matse tsam! a kirjina.  Yayin da yake yin nishin ni ma shi din nake yi. Lamarin da ya kara dagula mana lissafi gabad'aya domin yadda na yi masa ya k'ara kidimashi ainun! Ya sake rikicewa Yana ko'karin saka bakinsa cikin nawa. Ni da shi din gabad'aya muka kasa sarrafuwa domin kamar wad'anda aka haifa tare muka zama ita kanta kujerar da muke kai sai da ta jiki karshe ma rigib mukayi a kasan kafet wanda hakan ya zamo silar rabuwar gangar jikinkinmu  tare da dawowa hayyacinmu a lokaci daya.
 Bayan rabuwar gangar jikinmu sai ya tsira mini idanuwansa wanda babu alamun risina ko kunya a cikinsu.  Ni kuma sai hakan ya kara jefe ni cikin jin kunya da nauyi  har nake zargin kaina da bashi kwarin guiwa har ya aikata abinda ransa yake so. A ganina da tun farko na nuna ban yarda ba, ba zai samu sararin yin abinda ya yi ba. D'ankwalin abayata da ya sum'bule ya fadi a kasan wurin na d'auka na d'ora a kaina tare da dan gyara shi yadda zai rufe tudun kirjina, na tashi guiwa a sabule na kama hanyar fita kamar na rushe da kuka haka nake ji a cikin raina....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*

☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*12*

Ban kai ga bakin kofar ba sai na ji maganarsa. "Dawo gare ni Aminatu ka da ki fita."

Na dan tsaya gabana na harbawa sai ka ce yau ne karo na farko da jikina ya hadu da gangar jikin wani da namiji, wani irin yanayi nake ji a tattare da ni mai wahalar fassaruwa.

Sake maimaita maganarsa ya yi. A sabule babu wani kuzari da karsashi a tare da ni na ce." Mai zan yi maka to?"

Sai ya taso ya zo kusa da ni ya tsaya yana aika mini da wani irin kallo wanda ya sanyi gaggawar yin k'asa da kaina. "Ni ina sonki kuma ina buk'atar rayuwa dake, ina so ki gaya mini abinda yake cikin zuciyarki game da ni."

Shiru na yi ban iya ce masa komai ba. Sai kawai ya riko hannuna ya ja ni muka koma d'akin ya zaunar dani a gefan gado shi ma ya zauna garin haka wani dan karamin frem dake kan drowar gefan gadon nasa ya fado kasa.

Gabad'aya muka bi frem din da kallo, ya sunkuya ya d'auko shi yana gyarawa. Na tsirawa hoton da yake jiki ido shine da wata kyakykyawar mace nai matsakaicin girma, fara tas 'yar gayu, Ita dashi suna cikin walwala kuma rungume da juna.

Ya shafa hoton a hankali ya furta." Samira ce, na san baki santa ba ko." Kaina na kawar yayin da na ji wani abu na taso mini na ce." Ta ina zan santa."

Ya dube da frem din a hannunsa yana cewa." Daga tambaya, ai ko baki santa a zahiri ba zaki san sunanta, dama ina so na nuna miki hotonta idan mun daidaita junanmu ni dake"

"To." Kawai na ce masa babu wata walwala a tare da ni.

Ya cigaba da ce wa." Kin ganta nan, tana sona kwarai da gaske, ni ma haka lokaci guda mutuwa ta yanke mana k'auna."

kanzin ban ce masa ba. Yana ta yi mini tad'inta. Da dai na gaji na juya na dube shi a tsanake na ce." Ni kam zancan nan ya ishe ni haka, Allah Ya jikinta da rahama."

Hajiya wannan littafin na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba, hakki dai sunansa hakki komai kankantarsa mu kula sosai.

"Amin Ya furta yayin da fara'ar fuskarsa ta gushe kamar bai ji dadin maganata ba. Yadda na fahimta ya so maganarta ta yi tsayi a tsakaninmu na katse shi, Haka kawai na ji bana son maganarta duk da ta mutu amma ai har yanzu tana cikin ransa, to idan ba ya raina mini hankali ba akan me zai dinga yi mini maganar tsohuwar matarsa har yana gaya mini irin soyayyar da suka yi. Ai babu dadi ma ni ma na soko masa da maganar Yaya Aminu, wanda nake ganin babu wani d'a namiji da zan aura a yanzu ya kere masa.
Sai kawai na tashi domin barin d'akin kuma har na fita bai ce mini na dawo ba. Kenan hakan ya nuna ko ya samu hadin kaina mun daidaita duk sanda ya tuna matarsa sai ya shiga irin wannan yanayin. Ni yadda na fi tunanin lamarin kamar akwai yaudara irin ta d'a namiji. A ganina soyayya daya ce kuma naga zahiri yanzu tana wurin Samira, ni din yana so ya mori jikina ne shiyasa ya mayar da kansa mutumin kirki salihi, saboda namiji idan yana son abu duk dabaru ya iyasu. Yana sha'awata sosai ni naga zahiri, amma ai ban tona zuciyarsa naga shin da sona a ciki ko babu.

Tun daga ranar na dan janye jikina dashi. Ko na shiga duba shi ba na sakin jiki, balle har ya kusance ni, ko ya kai hannunsa jikina, kuma har yanzu frem din nan kusa da gadonshi bai d'auke ba, a ganina kamar da cin fuska a lamarinsa.
Ranar juma'a na shiga domin gaishe shi yana kwance idonsa a rufe. don ko sallamata ma bai amsa ba. Na dan zauna gefan k'afafunsa ina fad'in." Baba Ina kwana ko baka tashi ba ne?"
Ya bude idonsa wad'anda suka dan risina kad'an akwai alamun bacci a cikinsu da kuma damuwa. Kallona yake yi bai ce mini komai ba. Na dan sassauta fuskata domin ko na yi nufin yi masa rashin kunya ina tuna alherinsa akan yarona. Cikin kulawa na ce." Ko jikinki ne?"
Ya girgiza kansa kamar karamin yaro a hankali ya ce.'' Duk gabobina ne suke ciwo abinka da tsoho ai na ji sau'ki yau ma zan fita in sha Allahu."
"To kasha magani mana ko zaka ji sauki, dama kuma dole jikinka ya yi ciwo tunda tsayin kwana biyar kana gida baka fita ba sannan baka motsa jikinka ba."
Kwanciyarsa ya gyara yana ce wa." Ba wannan ba ce matsalar Amina tsufa ne ya fara tunkaro ni shekaruna hamsin ba d'aya fa.''
Murmushi kawai na yi na ce" Baba kenan." Na sunkuyar da kaina saboda ba zan iya jurar duban da yake yi mini ba.
D'akin ya yi shiru na 'yan mintina kwata kwata na kasa daga kai na dube shi saboda nasan ni yake kallo ban sani ba ko hakan dabi'arsa ce ko Kuma ni kadai yake yi wa oho, amma tun haduwata dashi ta farko na fahimci yana da kallo.
"Amina." Na ji ya kira sunana. Na amsa a hankali tare da kundumbalar dubansa.

"Ki dan yi mini tausa mana." Ya fad'a idonsa a tsaye a kaina.
Ban yi masa jayayya ba na ce." To." Amma a raina na kudire ba zan bari wani abu ya gifta ba.
Ya gyara kwanciya yana fad'in." Na gode sosai. A hankali na dora hannuna akan bargon ina matsa masa kafafunsa. Ya yi cilli da bargon yana fad'in "Ai bargo ki ke matsawa wannan." Ni Kam saurin sunkuyar da kaina na yi domin ganin kirjinsa a bud'e ashe ko riga babu a jikinsa sai gajeran wando. Na ce." To ka sanya rigarka gaskiya." Na cire hannuna tsam daga kan kafafunsa.
Ya dube ni yana fad'in." Dalili dame zansa riga Amina Ina ruwanki da rashin rigata ke dai kawai ki matsa mini kafafu zan nuna mini inda yayi mini tsami a jikina sai ki danna mini."

Ban ce masa komai ba na fara danna masa kafafu tafin kafa izuwa guiwarsa... "Yawwa sannu Allah Ya yi miki albarka." Abinda yake fadi kenan ya yi da yake lumshe idonsa. Ya bude yana kallona ya nuna mini kugunshi yana cewa.'' Nan da nan, duk ki danna mini za ki samu lada ba kad'an ba."
Na dinga bin inda yake so na danna masa da kallo kugunsa ne da kasan cinyarsa wuraran gabansa. A iya sanina nan wurin baya tara gajiya dama idan jiki ya yi tsami to ga'bo'bi ne. ban kuma san yadda zan yi wurin matsa masa ba domin dole idan zan yi sai na rank'wafa kansa.
Jin shiru ban cigaba da yi masa tausar ba sai ya dago da kansa yana kallona. Na yi saurin sunkuyar da kaina kasa na ji shi yana cewa." Ko ba zan samu ba ne." A hankali na dube shi na furta " Ba haka ba ne ban san yadda zan yi maka ba dole sai dai idan juyawa can 'barin kayi."
Ya ce.'' Ai abu ne mai sau'ki sai ya juya daya barin yana kallon yamma. A d'arare na d'ora a hannuna a k'ugunsa na fara matsawa a hankali yana cigaba da sanya mini albarka. Ganin bai yi yun'kurin sake yi mini wani abu ba yasa na gyara zama a gadon na saki jiki ina matsa masa har kasan kafafunsa. A hankali yake ta sakin ajiyar zuciya can ya motsa kamar zai gyara kwanciyar na yi saurin cire hannuna. Juyowar da zai yi kawai sai ya sanya hannuwansa duk biyun ya ratsa kwankwasona ya janyo ni da k'arfi ya d'ora kansa a cinyata.
Cikin faduwar gaba na fara ko'karin yakice jikina amma ban iya ba saboda ya rike ni da kyau. Gabad'aya na diririce shi kuma yana ta naninkata da kyar na iya fad'in." Don Allah ka cika ni."
Girgiza kansa ya yi yana wani irin nishi kamar wanda mugun zazzafi ya kamashi. Na rasa yadda zan yi kawai sai hawaye suka balle mini, ban san me mutumin nan yake nema da ni ba. Ya dago kansa yana kallon yadda hawaye ke zuba a kumatuna. A sanyaye ya furta." Me na yi miki?"
Na shaki hanci cikin kukan na ce." Ka rirrike ni ka sake ni, ai tausa kawai kace na yi maka."
Ya yi wani murmushi mai sauti Ido a lumshe ya ce." Ke fa ba yarinya ba ce Amina, zuwa yanzu ya ci ace kin gane ina bukatarki, amma daga an tabaki sai kuka bayan na fahimci kema kina da buk'atata."

"A a wallahi ni kam ba na da wata buk'ata." Na fad'a ina dan ture kansa da ya d'ora a saman kirjina. Na ji maganarsa a sakarce yana cewa." Ni kam yau sai na kawar da damuwar nan Amina, na kwadaita dake sosai." Ya sake matse ni gam yana shafa bayana.

A tsorace na ce." To ai ba a auna ni ba."
"Na fasa na yadda dake na fasa turo kowa ya auna ki." Yafad'a yayin da yake ta yun'kurin kwantar da ni ya hau bisa jikina.
Tsoro ya gama mamayeni ganin da gaske yake yi sai kawai na bud'e baki kamar 'kan'kanuwar yarinya na fara rere kuka ina buga kafafuna a gadon. Hakan ya kara kidima shi fadi yake yi. "Ni ne d'an koyo Amina, za ki taimaka mini ko? Ai ni ne ma zan koka don Allah ki d'ora ni a hanya." yana magana yana kwabe mini kaya yana kuma ta'ba wasu wuraran da suka yi masa a jikina.
Kada ku ga lefina tunda fatar jikinmu ta riga ta hadu wuri d'aya notikan kaina suka kwance. Wata masifaffiyar sha'awa ta tunkaro ni gadan-gadan. Sai na kasa katabus domin alwashin da na yi wurin hana shi kusantata a take ya rushe dalilin kalar soyayyar da ya fara gwada mini da kalamai da wani irin rarrashi na ban mamaki. Yana gaya mini shi dan koyo ne na taimaka mashi amma yanayin yadda yake sarrafa ni, shi ya tabbatar mini da cewa wayayyyan mutum ne, kuma ma'abocin soyayya. A yadda yake fadi bai ta'ba sanin mace ba ya yi irin hakan ina ga ni din da na san yadda abin yake. Kasa control din kaina na yi, gabad'aya na ki'dime domin tunda uwata ta haife ni na yi aure biyun nam cikin Ya Aminu da Alhaji Muntari babu wanda ya ta'ba gwada mini fitinanniyar soyayya a shimfida irin yadda dattijon nan yake yi mini. Sai na ri'ke shi hannu bibbiyu domin na riga na fahimci cewa da taimakona a wannan ga'bar zamu jiyar da kanmu dadi mara misaltuwa. Yana yin kalar nasa sambatun ina yin kalar nawa har Allah Ya sa muka samu gamsuwa nutsuwar da ta yi kaura daga gangar jikinmu ta dawo. Sai kuma kunya ta rufe ni, na kasa had'a Ido dashi yayin da shi kuma yake ta kallona yana murmushi da furta alhmdullhi alhmdullhi alhamdulillahi. Farincikinsa da murmushin da yake fuskarsa  shi zai nuna maka cewa ya samu irin gamsuwar da yake muradi. Ni kam hakan ya faranta mini raina mutuka da gaske. Yadda yake nuna murnarsa kamar wanda ya 'bare sabuwar budurwa a leda. Sai ya ba ni tausayi don ganin bai nuna takaici ko tsana ba a lokacin da yake auratayya da ni, nunawa yake har zuciyarsa ya cikin nishadi. Hakan ya kara tabbatar mini da cewa da gaske yake bai san buduruci ba, domin kuwa da ya san shi ko yaya ne zai nuna kishinsa a zahiri. Ya karbe ni a yadda nake kuma yana godiya ga Allah. Sai kawai k'walla ta ciko idona sonsa da tausayinsa suka dirar mini a zuciya. Na sa hannu na goge hawayen da ya gangaro a kumatuna Ina sake tuna irin addu'ar da nasha a wurinsa a d'an takin lokacin da ya wuce sai kace shi kadai abin ya amfana, duk ya ki'dime wanda ni kaina  na shiga sau'kin kasancewa tare dashi kuma na samu gamsuwa sosai. Haduwarmu a yanzu na tabbatarwa da kaina cewa na hadu da gwarzon namiji ma'abocin soyayya da son hutawa. Zan yi kokarin ganin

na yi masa biyayya a zamantakewar auran da zan yi a gidansa kuma zan zauna dashi domin Allah da manzonsa......

Hum ko zaman zai yi dadi a tsakaninsu ohi! Ga sh dai sun zama abu daya kuma sun gamsu da junansu. Zama zai mik'a ko ya zata kaya😃
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*13*

Cikin d'an 'karamin lokaci muka yi wata irin sha'kuwa ta ban mamaki muka 'kulle sosai muka zama da tib da taya, idan ka ga yadda muke shan soyayya sai ka rantse da Allah cewa auran soyayya muke yi dama tunfil'azal muna k'aunar junanmu. Wasu lukutan idan na zauna sai na yi ta mamakin kaina ganin yadda cikin kankanin lokaci mutumin nan ya saye mini zuciya domin ni kadai na san abinda nake ji a kasan zuciyata game dashi. Na mamaki na kuma yi wa kaina dariya.
Shi kansa Yusi sai ya k'ara kasancewa cikin farinciki mai tsanani wato ko a da can yanayin zaman da muke yi yana damunsa dan dai yaro ne bashi da yadda zai yi. Maganar wani gwaji ai tuni ta rushe bai kara tayar da ita ba, kuma duk dare sai mun yi auratayya abin ya zame mana jiki ma, idan yana gida mun dinga rungume juna kenan wasu lukutan har da rana ba ma iya ha'kura sai mun yi, idan dare ma ya yi mu sake yi. Ni dashi ba yara ba ne, yana akan matakin bukatuwa ni ma ina kan buk'atata shiyasa idan zai neme ni sau nawa ba na gajiya abin har mamaki yake ba ni.

Kusan sati uku da shiryawarmu jikina ya sake curewa kibar dai tana sake nunkuwa sai na ta'allaka abin da kwanciyar hankali da kuma abinda yake zuba mini. Abin ya dinga damuna domin jikina mugun nauyi yake yi mini ga wuyana yana nokewa, yadda na lura shi kuma jikin nawa a hakan bashi sha'awa yake yi, idan muna sex ma ya dinga luguigiutawa kenan.
Ganin yadda na daga hankalina da hakan sai ya fara rarrashina yana cewa shi ai na fi burge shi a hakan. Ni kuwa na ce ban yarda ba bayan tuntuni ya

nuna za'binsa ya fi son siririyar mace, ai don dole nasa shi ya d'auke hotonsa da Samira ya bud'e dorowa ya ajiye shi domin kullum sai na yi masa complain akan hakan, ina kasa boye kishina akansa a wasu lukutan ma idan yana waya da ma'aikatansa mata kasa jurewa nake yi har sai na tanka, idan ya yi mini shiru sai na yi ta takalarsa da fad'a baya biye mini.
Ba don ransa ya so ba ya amince mini hawa gym d'insa don shi a son ransa na zauna na lukuce domin ya ji dadin mutsukar naman jikina.

KANO
"To Hadiza ya za mu yi ne? tuntuni na gane yawon malamai ba zai amfane mu da komai ba. Ke kuma kaddararki a haka take domin idan kin tada balli mijinki ya sake ki don kina hangen kema ki samu miji irin na Amina Ina ganin da kamar wuya ba fata nake yi miki ba ba, don ni kaina na so a ce daya daga cikinku ne wata take auran Alhaji Tajo, to ba haka Allah ya tsara ba, kuma kin ga yanzu Amina ta yi wa kowa nisa a gidan nan kamota zai yi wahala gaskiya don tana da zuciya mai kyau." Ummansu Hadiza ce take wannan maganar cikin alhini da damuwa. Duk da cewa a yanzu ba su rasa komai ba sakamakon taimakon da Amina take yi wa Babansu ta hannun Hamusu Amma har yanzu idan hassadar ta motsa ita da yaranta sai sun kuka game da yadda Allah ya suturta Aminar da taguwar arziki.

Hadiza wadda ta yi firgai-furgai sakamakon irin bakar wahalar da take sha a gidan mijinta dalilin rashin haihuwa da kuma karayar arziki da mijin ya samu tuntuni sai kame kame yake yi idan ya bada na safe to fa ba zai bada na rana ba, idan kuma ya bada na rana to ba zai basu na dare ba, kowace mace a gidan tana cikin albarkacin yaranta da suke fita su nema. Ita Hadiza bata haifa ba shiyasa take ganin tasku a gidan, wataran haka take kwana da yunwa ko kuma ta zo gidan nasu ta ci sa'annan ta tafi da dumame. Dalilin da ya sanya kenan take yun'kurin kashe auran nata domin a ganinta idan ta fito tunda ba d'a ba jika itama zata fantama ta nemi kudi irin na amina har dai Allah yasa wani gwaska mai 'ya'yan banki kwatankwacin mijin Amina ya zo ya aure ta

Hancinta ta shak'a ta sanya hannu ta goge gumin fuskarta kana ta ce." Umma na gaji ba zan iya ba wallahi tallahi hakurina ya kare sai na kashe auran nan na fito, ban fa haihu ba, amma sai na zauna wahala ta kashe ni, don Allah ki bi ni da addu'a kawai, da sauran kuruciyata har yanzu dalilin da ya sanya ma kenan nake so na kashe auran na fito, munufar zuwa wurin Malam Lurwanu kuwa domin ya yi mini taimako akan Amina kafin na tunkareta don Ina so idan aurena ya mutu na je can Legos din wurinta na murmure sannan na samo jari mai tsoka ni ma na zo na fara business to kin san Umma kafin hakan ta faru dole sai an d'aure mata baki duk abinda na nema a wurinta ta yi mini, shiyasa fa na zo ina neman shawararki."

Gudun aure na kudi ne kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Umman tasu ta sauke numfashi tana ce wa." To ai ban ki ba Hadiza, ni na riga na dawo daga rakiyar Malam Lurwanu domin a da can wane irin kudi ne ba mu kashe ba amma babu biyan buk'ata, ko kin manta lokacin da muka je masa da bukata akan Uwargidanki matar Alhaji Halilu. A lokacin ne fa na d'aga gidana na gado da rage mini na sayar domin a samu biyan buk'ata. Amma da yake macuci ne babu abinda ya canza haka ya karbe mini kudi dubu dari uku da tamanin, sauran kudin suka watse a banza ba tare dana fargaba har yanzu kuma Hajiya Indo tana nan zaune daram da 'yayanta babu abinda ya same su." Shiru ta yi tana gyada kanta tabbacin har yanzu da haushin hakan a cikin ranta sai ta nisa kafin ta cigaba da ce wa."
Sai dai ki binciko wani malamin amma na yi Imani da cewa Malam Lurwanu kudinki zai ci a banza a wofi, bayan haka ma wai da wane kudin za ki tafi yawon malamai ne Hadiza, kayan dakinki duk kin sayar da su ko kina da wata kadara ne ban sani ba?"
"Katifa ta zan sayar sai kwanukana zan kai su rimi idan na hada kudin akwai wata mata amma gaskiya ita bori take yi da aljanu take aiki, tana watsa wuri ne kuma wallahi an ce ta iya zan nemi Bilki 'kawata sai ta raka ni mu je, ni ba zan yi abinda zai sabautata ba, kawai dai a sanya mata tsorona da kuma bin umarnina shikkenan abinda nake buk'ata dan gaskiya ina buk'atar jari na fi so duk buk'atar da naje mata da ita ta amsa mini babu jayayya."

Jiki a mace Umman tasu ta furta." Ki dai bi a hankali Hadiza ba zan hana ki ba, amma kada garin neman gira a rasa Ido, itama Aminar na tabbatar da cewa ba zaune take ba, kin san tun tana gida bata wasa da addu'a yawan yin sadaka da saukar al'kur'ani maigirma, kin ga kuwa tunkarar irinsu sai mutum ya shirya"

"In sha Allahu Umma zan yi nasara ke dai ki bi ni da addu'a kawai, ni ma zan gwada sa'ata wata'kila ma wanda zan aura sai ya fi nata wallahi."
Umman tasu ta girgiza kai da wani ma'kalallan murmushi a fuskarta da take nuna maganar 'yar tata lallai da kamar wuya wai gurguguwa da auran nesa.
****
"Inna Uwani ta dubi 'yar uwartata da take yin waya cikin nishadi da murmushi a tattare da ita tana ce wa." To Amina ina nan tafe in sha Allah rabbi, Ina dai fatan duk kuna lafiya ina Yusuf ai ina shan labarinsa a wurin Babansa, magana daya biyu idan muna waya zai ce Yusuf ya ce a gaishe ni."
Inna Uwani ta kawar da kanta zuciyarta fal takaici da zullumin yadda za ta yi ta raba wannan sha'kuwar da take tsakanin 'yar uwarta da kuma surukartata. Babbar damuwarta yadda yayar tata take nuna mata zahiri bata son d'anta ya auri 'yarta Hauwa. Ta san ta yi kuskure a can baya lokacin da suka nemi ita Hauwan ta maye gurbin 'yar'uwarta Samira bayan rasuwarta. Mutane suka yi caaaa! Kowa na fad'in albarkacin bakinsa mussaman daga can b'angaran mijinta cewa kada ta bashi itama zata mutu. A lokacin ne itama ta

rufe idonta ga-da-ga ta fito ta gayawa 'yar'uwarta cewa ba zata iya bashi Hauwa saboda an riga an ce mata aljana ce dashi itace masa silar arzikinsa Kuma ba zata ta'ba bari ya zauna da mace ba sai ta mutu.
To kuma yanzu gashi zaune da matarsa kusan wata biyar ba'a ta'ba bugo waya an ce musu bata da lafiya ba. Wannan dalilin ma yasa ta kara ji a ranta dole duk yadda za ta yi sai Hauwa ta maye gurbin 'yar'uwarta don har yanzu bata da tsayayye duk masu zuwa wurinta talakawa ne babu wanda ya kamo kafar Tajo kudi da d'aukaka.

Hajja ta dubeta tana ce wa." Uwani tunanin me ki ke yi ne? Ina ta magana shiru kin tsirawa wani wuri Ido." Ta dawo hayyacinta cikin diriricewa ta ce." Hankalina ne ya yi gida wallahi na kuma gaji da nan din tafiya zan yi a satin nan."
Hajja ta ce." To ba lefi Hakan na so a ce zaki zauna har lokacin dana shirya zuwa gidan Tajo din sai mu je tare, yanzu nan da muna waya take tambayarki na gaya mata gaki nan kusa da ni, ta ce a gaishe ki."

Cikin ya'ke ta ce." To Ina amsawa, ai ba ni ce matsalar ba Hauwa ce itace ta damu na dawo gida wai ta gaji da zama ita daya."
Hajja taja tsaki tana cewa." Ke kuma saboda kina jin tsoronta shine zaki kulle kaya ki tafi ko? Yarinya ce ita da zata ce tana jin tsoro, ina ce gidan naku na jama'a ne, koyaushe cikin hayaniya ake idan ta damu da ganin sai ta dauro kayanta ta biyo ki, kina nan kina jiranta."
Tana 'yar dariya take cewa." Ai ba a basu hutu ba a wurin aiki ba, kin san malamar asibiti ce, kuma suna da doka mai k'arfi shiyasa."
Hajja ta ce." Ai ban san ta fara aiki ba, amma dai duk da haka kya bari mu je mu dawo tukkuna idan ma zaki tafi sai ki tafi."

Ta ce." To shikkenan zan bari, amma ya maganarmu ta kwanaki akan auran Tajo da ita, har yanzu ina so zumunci nan ya kullu wallahi, Hauwa dai kamar Samira take kamarsu daya, duk abinda Tajo yake so a wurin Samira Hauwa tana dashi Hajja."

"To ai ba a nan take ba Uwani. Idan ya kasance Hauwa da Samira suna kama hali fa? Ai kowa da nasa. Na san halin kowacce daga cikinsu, Samira tafi Hauwa d'a'a, da girmama mutane bata da hayaniya, Hauwa kam ai tun tana yarinya ki ka lalata Uwani, ba zan iya cewa komai ba, anan amma ba zan hana ki yin magana da d'anki ba, tunda naga kun fara yin maganar ranar da zai tafi da iyalinsa. Idan kun hadu sai ki tambaye shi, idan ya amince shikkenan, sai mu yi musu fatan alheri da zama lafiya ."

To hakan da Hajja ta fad'a sai ya sanyaya mata rai, wanda a da take ganin kamar ba ta son ayi auran. Idan kuwa hakane Tajo ba shi da matsala tunda tun can ma ba kasafai yake yi mata jayayya ba. Amma dole sai ta yi kwantan b'auna ta daina nuna k'yamar auransu da matarsa a fili muddin tana so

hakanta ya cimma ruwa. Da wannan suka rufe maganar suka shiga wata wadda ta shafi zumuncinsu

***

Yau asabar tun bayan da ya dawo daga sallar asubahi ya kashe wayoyinsa ya kwanta bacci. Har na gama duk abinda nake yi bai tashi ba, abokin nasa ma Yusi da ya gaji da jiran saukowarsa fita ya yi harabar gidan wurin masu aiki domin d'ebe kewa. Kowa ya san Yusi a gidan dalilin saurin sabonsa da kuma da yadda maigidan ya daukake shi.

Kananun kaya na sanya a jikina na shafe ko'ina da humra ta ta mussaman....08089965176 sannan na dora abaya a kan kayan, na sake komawa dubawa ko ya tashi.
Yana nan a kwance a gado  yana bacci, daya saura minti arba'in. Na zauna a gefansa a nutse nasa a hannuna kan saisayayyar sumarsa wadda tsalli tsallin furfura ta fara bayyana ina shafawa a hankali murya can kasa na ce." Baba ka tashi rana ta yi....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE.*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin

nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*14*
Ya bud'e idonsa a hankali yana dubana. Na cigaba da shafa kan nasa ina kallon cikin idonsa na sake cewa." Karfe daya saura yanzu za a yi kiran sallar azuhr"
Hannuna ya rike ya had'a yatsunmu wuri d'aya bakinsa yana motsi na gane addu'a yake yi kafin a hankali ya tashi zaune yana fuskantata ya ce." Bacci na ke yi mai dadi da mafarkinki"
Ina murmushi na ce." Haba, ai gani a tare da kai?"
Ya d'aga mini girarsa." Wallahi na yi mafarki kin haihu."
Na zuba masa ido da murmushi a fuskata na ce." To me na haifa?"
Ya gyada kansa." Wannan kuma Allah bai nuna mini ba, ni dai kawai naga kin haihu hannunki ri'ke da jariri a cikin towol."

Na girgiza kaina ina raya abubuwa da yawa a cikin zuciyata. Ni kaina Ina so na haihu dashi ba na k'yamar hakan kamar Alhaji Muntari. Kuma ba ina so na haihu da Alhaji Tajo don dukiya ba, a a sai don bashi farincikin da yake muradi a koyaushe..
Na dube shi a hankali na ce." Baba ko dai don kasa hakan a cikin ranka ne shiyasa kake mafarki."
Ya girgiza kansa yana cewa." Ko kad'an, ai tunda na aure ki ban ta'ba mafarkin kin haihu ba sai yau, wata'kila Allah ne ya amshi adduata."
Shiru kawai na yi Ina kallonsa fuskata ba ta canza daga yanayin da take ba. A tsanake na furta." Ni ma zan so
hakan Baba."
Ya yun'kura ya sauka daga gadon ya nufi bandaki yana fad'in." Allah zai cika mana burinmu amma dai zan kara zage damtsena."
Dariya ta kwace mini na bishi da kallo yana ko'karin bude bandakin ya juyo yana dubana ya ce." Kina yi wa dattijo dariya ko Amina."

Na ce." Wane irin damtse zaka sake zagewa Baba kana fa kokari kawai dai Allah ne bai kawo ba."
Ya ce." Zan dai zage na gaya miki."
Na ce." To shikkenan." Ya bude bandakin ya shiga, ni kuma na tashi na gyara shimfidar gadon tun bayan shiryawarmu ban sake bari wani ya gyara masa d'aki ba.
Na d'ibi wayoyinsa na dora kan dorowa sannan nasa freshnar. Na zauna har ya fito daga toilet din yana tsane jikinsa yake fad'in." Kin ga na tashi da wata irin yunwa Amina, ko yau daya zaki tuka mini towon dawa, na ci girkin amarya."
Na ce." Me zai hana sai na shiga kicin yanzu, daga yau ma zan dinga yi maka girka.
Ya furta." Da kuwa na ji dad'i."

Littafin gudun aure ne na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na tashi a hankali na isa inda yake ya na ta shafa mai a sannan jikinsa na lakaci wani a hannuna ina fad'in." Bari na shafa maka a bayanka."
Shiru ya yi bai ce mini komai ba har na fara shafa masa man yana ta kallona ta madubi sai na ga ya dan rintse idonsa ya bud'e ya dube ni ta mudubin muka had'a Ido, sai ya daga mini gira yana fad'in." Alwalata zata karye Amina bar shafa man nan. Yanzu idan na ce zan take ki zan yi asarar jam'i a massalaci, amma idan na dawo za mu had'u."
Da sauri na cire hannuna daga wuyansa na ja da baya ina cewa." Ai ban san kana d'aure da alwala ba."
Ya ce." Ba za ki sani ba dama tunda ban gaya miki ba."

"Hakane bari na shiga kicin din Baba." Yana ko'karin fito da jallabiya daga ma'adanar kayansa ya ce." To Allah Ya yi miki albarka."
Na amsa da "Amin." Sannan na bud'e d'akin na fita cikin nutsuwa.

Da yake duk wani nau'in abin buk'ata akwai ban sha wahala ba wurin sarrafa masa abinda ya bukata. Na kammala komai tsaf na shirya a babban tire na d'auka na fita daga kicin zuwa lokacin na san ya dawo daga massalacin. hakane kuwa yana saman sofa yana duba laptop wadda take kan cinyarsa. Na dora tire din abincin a tebur din da yake gabansa.
Ya dube ni da murmushi a fuskarsa ya furta." Sannu.'' Na amsa cikin kulawa kafin na nemi wuri na zauna ina kallonsa ya a rufe Laptop din yana tattare hannun rigarsa yana cewa." Yau zan ci girkin amarya.
Na yi murmushi a nutse na fara had'a masa. yana cewa." Tun kafin ma na ci miyau na ya tsinke, na kwana biyu ban ga irin wannan towon dawar ba."
Na ce ." Idan ma kana so sai na baka a baki."
Ya dube ni yana dariya ya ce." Da na ji dad'i kuwa.
Ban ce komai ba da na gama hada abincin na zauna daf da shi da flat din a hannuna na gutsuro tuwon tare da dangwalo miyar na ce." To bude bakinka."
Da sauri kuwa ya bude bakin na ce." Yi bisimillah." Ya yi da sauri yana yi mini wani irin kallo sai murmushi yake yi. Nasa masa towon a baki ya fara taunawa idonsa gabad'aya a kaina. Ya ce." Yau kin yi mini kyau fa my wife."
Na ce." Ni ma haka my love dina."
Yanayin yadda nake tarairayarsa yana mutukar kidima shi don a daddafe ya gama cin towon sai kai hannunsa yake jikina wai dole sai ya cire aftar dress din dana dora a kan kananun kayan. Idonsa kacokan akan kirjina. Ni kaina na san breast dina na bashi sha'awa don har sai da ya gaza yin shiru wataran yake cewa da ni kamar ban ta'ba shayarwa ba. Bashi da rufi ko kad'an, ko a wurin sex ne baya k'wange kuma baya yin shiru yana nuna nishad'insa sosai. Ni kam bai bari ma nasa komai a cikina ba ya kidi'ma ni da salonsa ban a iya turjiya ko jayayya don har ga Allah ni ma ina zumud'in kasancewarmu koda za mu yini zurr!

Bayan sati Hamusu ya kira ni yake gaya mini lokacin ziyararsu Kamalu ya yi, na ce ai kam wannan karon da ni za a yi tafiya. Koda na gayawa Yallabai din sai ya ce shima dashi za a je. Na kasa boye murnata  na rungume shi a kirjina kam ina sumbutarsa sai ya dora kansa a kirjina tare da matse ni a jikinsa sosai.

Alhamdulillahi dama komai ya yi farko yana da karshe, sannan babu abinda yafi karfin Allah. Yanayin yadda muka samu Kamalu ya faranta mana rai sosai, yaro ya nutsu ya kara girma da hankali, farincikin hakan ya sanya hawaye zubo mini na rungume shi Ina kuka. Shi kam banda murmushi babu abinda yake yi hankalinsa gabad'aya yana kan d'an'uwansa Yusi da shi ma murnarsa ta kasa buyuwa.

Har 'kasa ya durk'usa ya gaishe da kanin uban da kuma ogan tafiyar wanda shi ma ya dinga murmushi ya riko shi yana shafa kansa yana ta yi masa addu'a tamkar d'an cikinsa.

Sanin fuskarsa farin sani a duniya ya sanya tun daga bakin gate din jama'a ne har cikin makarantar malaman kuwa bakinsu ya kasa rufuwa.
Mun samu a k'alla awa daya da rabi a makarantar kafin mu yi Shirin tafiya. Yallabai din ya keb'e da shugaban makarantar suka tattauna muhimman abubuwa kafin ya yi wa dalibai da mahukanta tsangayar alheri mai dumbun yawa, ya kuma ce idan buk'ata ta taso ta neman taimako a tuntube shi.
Na d'auka da zamu tafi Kamalu zai nuna damuwarsa ko kad'an sai gashi shine har da rako mu bakin mota. Yusi kam sai goge fuska yake yi yana tafiya a hankali Baban nasa ya dube shi yana dariya yake tsokanarsa ko a bar shi ne a makaranta shima. Yayi shiru dai bai ce uffan ba ya je ya jingina a jikin mota yana kallonmu har muka gama sallama da Kamalu aka mayar dashi ciki.
Da yake Hamusu a makarantar muka same shi yanzu ma motarsa daban, amma sai da muka rage masa hanya zuwa babban titi tukkuna maigidan ya bashi dubu hamsin ya ce ya shiga mota domin komawa gida. Mukayi sallama dashi yana ce mini akwai abubuwan da yake so mu tattauna dangane da harkokinmu amma zai kira ni tunda yau lokaci bai ba mu dama ba.

Gamu a garin kano amma kiri kiri mutumin nan ya ki ya barni na gaisa da 'yan uwa da abokan nan arziki, ina so naga Babanmu Sahura da Kuma Hajja. Ya ce a a Hajja suna tafe ita da Inna Uwani a satin da zamu shiga. Dole na ha'kura direbansa wanda shine ya je ya d'auko mu daga airport ya mayar damu muka shiga jirgi muka koma gida tare da escort dinshi Sukajiru.
***
Mafarin fara samun rashin jituwarmu zuwan Hajja da kanwarta inna Uwani. Ba ni da matsala da Hajja tunda duk wata k'auna da kulawa ta nuna mini ita. Amma duk wasu hanyoyi da Inna Uwani take bullo dasu na sani tunda ni din dai ba yarinya ba ce. Duk motsin da zan yi akan idonta. Duk kuma maganar da zan fad'a sai ta juya mini ita ta gaya mini babu dadi mussaman idan Hajja bata wuri to inna Uwani ta dinga yar mini da magana kenan, ba ta yi a gaban 'yar uwarta da maigidan tana nuna musu ai tana kaunta. Hakan ya sanya ma ban cika zama a falon ba idan suna zaune har maigidan sai na yi zamana cikin d'aki wataran sai Hajja ta kira ni nake fitowa. Ba na son tashin hankali ko kad'an, kuma ba na so na raina ya 'baci har ta kaini ga mayarwa da matar martani wadda hakan na san ba zai yi wa kowa dadi ba. Shiyasa muddin da ita a wuri ba na fitowa. Yau satinsu biyu da zuwa amma na k'augata su tafi ba wai Hajja na gaji da ita ba sai ita inna Uwani wadda na gama gano take takenta maigidan ya kawo 'yarta cikin gidan mu zauna mu biyu tunda tasha fad'a girman gidan ya wuce ace mace daya ce a ciki ba mata hud'u ba

Shi kansa a tsukin nan haushinsa nake ji domin sai nake ganin kamar duk abinda matar take yi da saninsa kuma ko a fuska bai ta'ba nuna mata cewa bashi da ra'ayin auran Hauwan ba.
Abu biyu ya hade mini a lokacin guda habaice habaicen Inna Uwani da kuma rashin kuzarin da yake damuna. A satin da ya gabata ya kamata ace na yi al'ada amma ban yi ba,  na ji sauye sauye a jikina da yawa wanda ya sanya nake tunanin ko ciki ne da ni.

Yammacin ranar asabar ina kwance a d'aki na rufa da bargo zazzabi ne  ya rufe ni a sa'ilin don ma kada Hajja ta fahimci wani abu ne ya sanya na shigo d'aki na kwanta.  Kira ya shigo wayata dake saman dirowa, koda na duba maigidan ne, nasa a kunne ba tare da na ce komai ba. Haka kawai ko muryarsa ba na son ji domin sai nake ganin kamar akwai wani abu a zuciyarsa da yake boye mini. Zuciyata ta gama aminta da hasashen da nake yi akan cewa ya samu abinda yake so a wurina shiyasa ya rage ba ni kulawar da farko yake ba ni.

Shi ma babu sakewa a maganarsa yake cewa da ni na zo na same shi a samansa. Ban ce masa komai ba na kashe wayar na kai minti goma kafin na tashi da kyar na sanya hijabi na fito. Suna zaune suna kallo har da Yusi na dan saki fuskata. Hajjan ta dube ni tana tambayata bacci na yi ne, sai na bata amsa da cewa "E" kawai, ita kuwa inna Uwani a lalace ta dube ni kafin ta  kawar da kanta.
Na d'auke kaina ni ma ban tanka mata ba na wuce zuwa saman maigidan.
Na same shi a zaune Yana aiki da computer ban ce komai ba na zauna nesa dashi. Shi ma bai dago ba har sai da ya gama abinda yake tukkuna ya dube ni muka had'a ido. Babu sakin fuska ya fara tuhumata akan abinda ya gani a tare da ni wanda ya zama sabo a wurinsa. Tuhumata yake yi akan har raini ya fara shiga tsakaninmu.
Na dube shi zuciya na zafi na furta." Me nake yi maka na raini, sannan kuma wane canji ka gani a tare da ni da zaka tuhume ni akan hakan? Ni na gaji rayuwarta ta baya tafi mini dadi wallahi."
Ya zuba mini idonsa Yana kallo kafin daga bisani ya taso ya zo ya zauna kusa dani ya ce." Ni na kasa gane inda kika nufa a cikin kwanakin nan Amina tunda su Hajja suka zo ki ka canza mini ba kya ba ni kulawa babu tarairaya gaisuwa ma sai kin ga dama. Yau kwana takawas rabon dana had'a shimfida dake menene matsalar ki ne?"
Kawar da kaina na yi ban tanka masa ba. Ya sanya hannu ya juyo da fuskata muna kallon juna ya furta." Me na yi miki umm! ki gaya mini  sai mu samu maslaha ba na son fushin nan naki my love....
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta

Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH*
 □□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

 TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550

2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*15*

Nan da nan 'kwalla ta ciko idona ta fara zuba. Ina ina jin nauyin na ce masa ba na so ya auri zabin Yaddikonsa kuma kanwarsa, abinda yake ta damuna kenan, domin na gama fahimta duk kwane kwanen da Inna Uwani take yi kenan, shi ma kuma kamar yana da burin cika mata muradinta. A tunanina idan na nuna masa rashin amincewata na so kaina da yawa. To ni kaina na kasa sarrafa zuciyata domin wani mugun kishinsa nake ji a zuciyata ba kuma na so kowace mace ta rabi inda yake.
Ganin ina kuka kashir'ban sai hankalinsa ya tashi ya rungume ni a kirjinsa yana jijjigani kamar karamar yarinya sai ruwan kalamai yake yi mini a kunne. Wannan ma yana d'aya daga cikin dalilan da suka sanya ba na so wata mace ta kusance shi domin iyakar soyayya mutumin ya iya.
Daga rarrashin sai lamari mai girma ya gifta. Dama kuma akwai buk'atar hakan, tunda tun bayan shiryarmu ba mu taba kwana ba tare da mun kusanci juna ba. Sai gashi yau kwanaki takwas kenan babu wannan, shi din ma ya isa ya taka muhimmiyar rawa wurin dasa k'unci a zukatanmu. Ban dora alhaki akan kowa ba sai akan Inna Uwani domin itace take ko'karin rusa mana farincikinmu. To ko lokacin da muke biyawa juna buk'ata bai iya yin shiru ba. Yana gaya mini kamar yau din ya fara sanina domin ya gamsu fiye da kowace rana. Ni ma ban boye masa ba na nuna masa na yi kewarsa kwarai sa'annan kuma na gaya masa abinda nake hasashe na samuwar cikin da yake ta mafarki. Ai sai ya kara kid'imewa Yana ta addu'ar Allah Yasa shi din ne. Koda muka yi wanka muka sauka kasa kawai sai na ji yana gayawa Hajja cikine da ni. A okaci guda na diririce kunya mai karfin gaske ta kama ni.

Cikin jin nauyi da kunyarsu na yi kasa da kaina. Shi kam bai ji nauyi ba ya riko hannuna muka zauna a kujera yana fad'in." Ciki ne da ita wallahi, yanzu nan ta gaya mini, Hajja wannan ranar tarihi ce wajena ku taya mu addu'a Allah Ya sauketa lafiya.
Hajja baki a har kunne take cewa." Addu'a ta zama dole Tajo, ai ni ma ranar ta zama tarihi a wajena ba zan manta da ita ba."
Budar bakin Inna Uwani ta ce." Ina ce ita ba ta fari ba ce a wajanta ko."
Hajja ta ce." Kwarai kuwa ta uku ce, ai mu kamar ta fari ce a wajenmu Uwani."

Sai ta yi ya'ke wanda hausawa suke kira da ya fi kuka ciwo tana fad'in." To Allah Ya raba lafiya." Gabad'aya suka amsa da Amin. Ban da ni, da na tafi tunanin abubuwan da suke faruwa.
Samuwar juna biyu a tare da ni sai ya kara janyo mini k'auna da soyayya a wurin uwar mijina. Dashi kansa maigidan wanda a wasu lukutan har tausayi yake ba ni, idan na ga yadda yake kaffa-kaffa da ni, sam baya son b'acin raina.  Idan yana gida baya bari na yin komai kullum muna tare da juna a cewarsa yana jin d'umin abinda zai haifa.
Wasu lukutan har b'uya nake yi na share hawaye domin tunda cikin ya yi k'wari zuciyata take ta yi mini sa'ke-sake marasa kyawu. Koda abin ya dame ni na kira Anti Yagana a waya na gaya mata ina yawan mafarkai da munanan tunanai take cewa da ni mafi akasari masu ciki sukan samu irin hakan. Amma dai na dage da addu'a. Ni kam cikin Yusi da Kamalu ban yi irin wannan wasi-wasin a  raina ba.

Hajja ta samu wurin zama domin kuwa cewa ta yi ba zata tafi ba har sai na haihu tukkuna lokacin watansu hud'u da zuwa. Inna Uwani ta yi ta yi da ita su tafi tace mata a'a, sai na haihu. Sai kawai ita ta yanke shawarar tafiya domin dama kamar akan kaya take dalili ta tsani ta bude ido ta fa gilmawar matar gidan da ciki, da kuma yadda masu gidan suke ki'dime akan hakan. tana ganin komawarta gida shine maslaha a wajenta domin ta je su tattauna yadda za a yi, don ta fahimci kamar sai ta biyo ta bayan gida tukkuna ha'kanta zai cimma ruwa.

Tafiyar inna Uwani da kwana biyar. Anti Yagana da Hadiza suka zo. Anti Yagana sai da ta fara sauka a can gidanmu dalili ta kwana biyu ba ta je. Nan fa Hadiza ta ma'kale mata wai lallai sai sun taho tare. Sai a lokacin ma ta san auranta ya mutu tana cikin iddah ne. Da ta tambayata dalili duk ta kwashe komai ta gaya mata. A lokacin ta yi mata fad'a sosai irin na 'yan uwantaka. Ummansu tana zaune tana ji amma ba tace komai ba, ita bakin cikinta yadda a komai yaranta ne a baya. Kallo d'aya ta yi wa Yagana ta gane cewa lallai tana cikin hutu da jin dadi, dama kuma ko lokacin da ta auri mijinta mai rufin asiri ne.
Da sahalewar Babanmu suka kamo hanya suka taho. Maigidan kuwa ya dinga fad'a yana cewa mai yasa suka biyo motar haya daga Kano zuwa Legos ba su kira su sanar da ni ko kudin ticket sai a basu su biyo jirgi su zo.
Duk wani abu da ya dangance ni yana mutukar daraja shi da martaba shi. Tun da ya fahimci cewa anti Yagana itace babba a gidanmu yake girmamata gashi dai ya kusa haifarta amma idan zai gaisheta sai ya dan risina. Dalilin da ya sanya ma kenan ta guji zaman falo take zamanta a d'aki, takan ce mini Amina mijin nan naki kunyarsa nake ji wallahi tallahi wani idan ya ga abinda yake yi sai ya d'auka kin wanke kin bashi ya shanye. Ba na so jama'a su gazgata zarginsu akan cewa matan barno suna asiri. Kin ga dai mutumin nan babu wani abu da muka taba yi masa na mallaka, ban sani ba ko kin yi a boye Amina abin yayi yawa.

Na dinga dariya ina fad'in wallahi ko d'aya anti Yagana shi haka yake fa bashi da wani girman kai da ma'aikatansa sai ya zauna ya ci abinci dasu. Ni kaina dan ya durk'usa mini ba wani abu ba ne. Ta ce." Idan ya durk'usa miki wannan tsakaninku mijinki ne, amma ni kam ina kin kunyar abinda yake yi mini. Mutumin da manya suke zube masa amma idan zai gaishe ni sai ya rankwafa."
Na ce." Anti Yagana duk wanda ya dangance ni to wallahi yana da daraja a wurinsa. Karin abin ma kuma wannan cikin na jikina ya sake janyo mini girma a wurinsu da mahaifiyarsa. Wallahi ban yi masa komai na gusar da hankali ba."

Ta girgiza kanta tana fad'in. " Lallai Amina Allah ya share miki hawaye sai kiji tsoron Allah , ki kyautata masa kamar yadda yake kula dake, ki tsare masa mutuncinsa da dukiyarsa. Na tabbatar da cewa son da yake yi miki na Allah da Annabi ne, ki yi iyakacin bakin kokarinki wajan yi masa biyayya."
Na ce." In sha Allahu Anti Yagana na gode."
To duk wannan zantukan da muke yi Hadiza tana zaune ba ta ce komai ba illa zare Ido ta kalli bakin wannan ta kalli bakin wannan haka ta dinga tana ta sakin ajiyar zuciya. Hadiza kenan duk wani motsi da zata yi na san manufarsa domin kuwa tare muka tashi a gida daya daki daya, babu yadda zata yi ne shiyasa ta sakar mini domin kuwa Allah ne yake ikonsa.

Anti Yagana da Hajja jininsu ya hadu sosai idan suna hira tamkar uwa da 'yarta. Halinsu ya zo daya sannan kuma tunani da nazarinsu ya zo daya. Ina jin dadi sosai a duk lokacin da na gansu a tare suna hirarraki irin na rayuwa. Ita kuwa Hadiza dama ta samu bata aikin komai sai ci da kuma bacci abinda take so ya samu basu cika wata biyu ba ta murje ta yi bul daidai da fatar jikinta sai da ta canza. To ko yaushe tana cikin Ac ga abinci mai kyau.
Lokacin da anti Yagana ta shirya tafiyarsu sai Hadiza ta yi tsalle ta dire ta ce ba zata ta tafi ba sai na haihu tukkun. Hajja kuwa ta goya mata baya. Maigidan ma haka ya ce ta zauna tunda bata da aure. Ni dai ban ce komai ba domin na riga na san ba don ta kula da ni ta nace sai ta zauna ba domin biyan bukatarta ce. Na yi ta dariya ina kallonta a lokacin da suke ta jayayya da anti Yagana tana cewa ba haka Babanmu ya bata umarni ba, don haka dole sai sun tafi tare. Maigidan ya sauko daga sama da yake asabar ce baya fita da wuri ya riski jayayya. Ya ce anti Yagana ta yi hakuri zai kira Baban namu ya yi masa bayani. Ba don ranta ya so ba ta ha'kura. Aikuwa muna shiga d'aki ta rufe Hadiza da fad'a tana cewa." Ba zai yiwu daga zumunci mu tare musu a gida ba. Ina lefin wata biyun da mukayi ai ya isa. Tun Hadiza na daurewa har sai da ta fashe da kuka  tana cewa." Anti Yagana menene don na ce zan zauna na kula da 'yar uwata. Ba ni fa da nauyin kowa a kaina ba miji ba yara. Ko don ba ciki daya muka fito tare ba shiyasa zaki dinga nuna mini banbanci. Ko ina da wani aibu ne."

Cikin rashin jin dadin abinda Anti Yagana ta yi mata na ce." Hadiza ba haka ba ne, ba ki fahimci Anti Yagana ba, amma kada ki yi mata wannan fassarar

don Allah, menene babu komai ki yi zamanki mana, na gode sosai da kulawarki a kaina, Allah ya bar zumunci."
Anti Yagana tana jin mu ba tace uffan ba sai aukin tsaki da take ja. Na riga na gama fahimtar duk inda ta dosa. Tana jin tsoron zaman Hadiza ne kada ta zo ta aikata wani abin da zai sanya girma da mutunci mu ya zube a idon maigidan.

****
Duk wani shirye-shirye na tafiyar anti Yagana maigidan ya kammala mata domin cewa ya yi a jirgi zata koma gida in sha Allah dan ba kasafai ya fiye son tafiyar motar nan ba.

Gudun aure na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Saura kwana biyu ta tafi rikici ya balle a tsakanina dashi domin har ga Allah nayi iyakacin bakin kokarina wurin ganin na danne abin a zuciyata hakan ya gagara. Tun lokacin da muka sasanta jununmu nake masa soyayya ta tsakani da Allah irin wadda ba na so ko kuda ya kusanceshi. A zahiri tashi ce ta fito fili, amma ni gani nake yadda nake bala'in sonsa da kishinsa baya yi mini kwatankwacin hakan. Kuma ina ganin komai na rayuwata zan iya bud'a masa ya san dashi ba zan rufe masa ba, zan iya bayyana masa sirrina ganin yadda ya d'auke ni, da kuma matsayi maigirma da ya ba ni a zuciyarsa. Duk wanda zai ba'kunce mu na second guda zai fahimci cewa akwai k'auna sha'kuwa da mutuntawa a tsakaninmu. Dalilin da ya sanya ma kenan na ajiye hakan a raina cewa. Babu wani abu da ya dangance shi da zai boye mini sai gashi yau ya nuna mini cewa namiji ne fa shi kuma dabi'ar nan fa ta kumbiya kumbiya da Allah ya hallice su da ita ba zata canza ba. Hauwa dai yar uwarsa ce ni ban isa na raba tsakaninsu ba, amma wallahi ban taba tunanin suna waya ba domin bai ta'ba nuna mini hakan ba, yarda dashi ce ta sanya ma ba kasafai nake d'aukar wayoyinsa ba duk da cewa yakan ajiyesu a wurin da nake zaune ko ya tashi ya fita daga d'akin ya bar su. Da can na yi zarginsa dalilin abinda ya yi mini farkon haduwarmu, amma da zama ya yi zama a tsakaninmu sai na gazgata rantsuwarsa inda yake ce mini bai taba kusantar zina ba, kawai ya jarraba ni ne akan wata bukatarsa don samun abokiyar rayuwa. Ashe ha'kan Inna Uwani ya kusa ya cimma ruwa ban sani ba, ina ta zaune sake da baki.
Abinda ya faru shine bayan mun gama sunna sai bacci ya kwashe ni domin ba wuya bacci haka nake yi don yanzu ko auratayya muke yi bana wani katabus shi yake kidansa da rawarsa wasu lukutan ma ina gyangyadi zai kammala. Abinda ya faru kenan bacci ya kwashe ni, shi kuma ya shiga bandaki domin yin wanka. Cikin ikon Allah kiran wayarsa da akayi wadda take saitin kaina na bud'e Ido firgit sakamakon karar da ta cika mini kunne. Na tashi da sauri idona ya sauka kan fuskar wayar wanda sunan Dr Hauwa ya fito rad'au kan screan din. Gabana na bugawa na tsirawa sunan Ido a sa'ilin kuma na nemi baccin da yake cikin idona na rasa na yi tarmazai ina ta duba

sunan dr Hauwa. Ban d'auki wayar ba har sai da ta katse na d'auka na shiga wurin kira naga iya adadin kiran da tayi masa ba zai k'irgu ba. Na duba shi ma naga ya kira ta sosai. Na duba messages gasunan kala kala ta turo masa na gaisuwa da fatan alheri da kuma na soyayya Amma ba kowanne yake bata amsa ba domin kusan guda talatin bai fi uku ya rubuta godiya ba. Hakan bai sanyayar mini da zuciya ba domin na san ba kasafai ya fiye son rubutu ba ya fi kiran waya ko a Whasap ne sa'kkonin mutane sukan yi kwana da kwanaki kafin ya ware ranar da zai dubu su. Wasu ma baya reply sai dai ya kira mutum a waya.
Na ajiye wayar na koma na kwanta zuciyata na tsalle da tafarfasa. Ni kaina ban san haka nake da zafin kishi ba sai yau idona har ya ji yake yi mini wani 'kullutun abu ya danne mini makogwaro.
Koda na ji fitowarsa daga bandakin ban bude Ido ban kuma motsa ba. Ina jin lokacin da ya d'auki wayar ya zauna saitin kafafuna yana dubawa ban bud'e idona ba amma duk wani motsinsa Ina ji.
Kawai sai na tsinkayi maganarsa yana cewa." Hauwa ya kike, ina wanka ne lokacin da ki ka kira, Ina inna Uwani ya aikin naki."
Ashe kiranta ya yi domin a tunaninsa bacci nake yi.
Tana tsaka da bashi amsa na bud'e idona tare da tashi zaune Ina kallonsa. Ya dube ni yana fad'in." Bari zan kira ki an jima sai mu yi maganar oke."
Ya kashe wayar ya ajiye yana fad'in." Madam tashi ki yi wanka mana."
Na dube shi fuska a turbune...." Menene na katse waya da sauri kana cewa za ku yi magana an jima. Hauwa ce fa, to menene abin boye mini, ko ni din na isa na hana ka ka aureta ne.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu.

Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*16*
Ya girgiza kansa yana ce wa." Ba ki isa ba, muddin ina da ra'ayinta. iko kuma ina dashi, bayan hud'u har 'kwarkwara zan iya yi."
Na ce." Haka ake son namiji ai, dama ai na jima da sanin target dinka Yallabai, don girman Allah ka auro ukun a lokaci daya to me zai dami Amina."

Ya jima yana kallona da fuska irin ta b'acin rai. Yana da juriya a wasu lukutan idan sa'insa ko rigima ta had'a mu yakan sakar mini ya share duk maganganun da zan ya'ba masa kuwa. Amma a wasu lukutan yakan yi fushi ya kuma nuna mini b'acin ransa. Yadda na fahimta  tsayayayyar da nake masa ta fara tunzura shi.
Ya furta." Ki shiga hankalinki fa Amina, ki daina ganin kamar na mayar da kaina sauna akanki ki nemi ki yi mini rashin kunya zamu sanya kafar wando daya a tsakaninmu. Tabbas ina sonki amma hakan ba zai sanya na zuba Ido kina cin kasuwa a kaina ba, ke ba ki da aiki sai bakin kishi, motsi kad'an sai kin tuhume ni,  haifata ki ka yi da zaki dinga titsiye ni da maganganu irin wannan. Na gaya miki ina da ikon mata hud'u a yanzu. Ba zai yiwu Allah Ya halasta mini abu ba wata mace ta tsorata ni ba. Ni ba sakaran namiji ba ne. Hauwa k'anwata ce, kuma ina da damar auranta a yanzu muddin inda ra'ayin hakan so ki samawa kanki nutsuwa tunda ban tauyeki ba."

Na ce." To ka fito fili ka fad'a mana zaka auri Hauwa sai me? Ai ni dama ban ce ni din 'yar'uwarka ba ce, to me ya had'a ni da kai dama in banda k'addarar aure. Me ya hanaka auran Hauwan tuntuni. Matar da ita da uwarta suka guje ka a baya sai yanzu zasu dawo rayuwarka saboda wata manufa. Idan zaka auro duk 'yan gidansu Hauwa bai dame ni ba wallahi." Na kàrasa maganar ina buga cinyata da yin wani irin nishi!

Cikin fusata ya buga katifar gadon na dan tsorata kuma gabana ya buga na matsa gefa. Fuskarsa ta canza sosai da fushin da ban ta'ba ganinsa a ciki ba. Ya ce." wallahi kin ci arzikin abinda yake cikin ki amma da ba don hakan ba sai na sa'ba miki, ni za ki dubi tsabar idona ki gayawa magana dan Ubanki, ban haifeki ba. Inna Uwani sa'arki ce, ko ni zan iya duban tsabar idon mahaifinki na gaya masa magana. Na taba cin zarafin wani a halinki  baki da mutunci ko Amina, kin ga damata kina gaya mini duk abinda kike so zan baki mamaki."
Duk maganganunsa ba su yi mini ciwo illa zagin da ya yi mini hawaye ya b'alle mini  ina kuka nake ce wa. " Ni kake zagi ko? Ai duk a cikin maganganuna ban yi maka sharri ba, gaskiya na fad'a kuma ban zage ka, amma ka dubi tsabar idona ka zagi Ubana, ka haife ni ne?"
Tsaki ya ja mai karfin gaske ya tashi ya fara hidimar sanya tufafi a jikinsa. Lokacin Hauwan ta sake kiran wayar amma bai yi yun'kurin d'agawa ba, na ce." Ka zo ka d'auka mana 'yar uwarka jininka tana kiranka a waya, ni bana son munufarci.
Bai saurare ni ba sai da ya gama shiryawa tukkuna ya zo ya zauna a kusa dani ya d'auki wayarsa ya kirata.  Muryar da ni kadai yake yi wa amfani da ita idan muna bargo daya da ita ya yi wa Hauwa magana......"My love menene uhmm!  ki samu nutsuwa za a yi, in sha Allah akwai maganganu masu muhimmanci da zan tattauna dake in sha Allahu idan na samu sukuni karshen watan nan zan zo bauchin sai mu tattauna ki gaishe mini da Inna Uwani."

Tana bashi amsa ya tashi da wayar a kunnansa ya kama hanyar fita. Cikin gaggawa da mugun sauri na yi nufin dirowa daga gadon bargon da yake kafafuna ya tad'e ni na fado rigib!
Ya juyo a razane a lokacin ni kuma na yun'kura na tashi duk da ciwon da jikina yake yi mini hakan bai hana ni tunkararsa ba. Da sauri ya bude kofar ya fita dan yadda ya nuna mafisar ta ishe shi haka in ba haka ba ya tsaya mu yi mana. A baranda na riske shi don bai kai ga sauka ba. Na ri'ke shi ta baya kamar mai shirin yin kokawa. Zuciyata sai tunzura ni nake yi, na rasa wane hukunci zan yi masa kuka kawai nake yi na ri'ke shi katamau! Hankalin Hajja da Anti Yagana ya yo saman domin gunji nake yi ba kad'an ba.
Shi kuma duk ya diririce! Sai kamo ni yake ko'karin yi yana cewa." Ki bi fa komai a hankali, kin ga an yi ne? da za ki tayar da hankali, ni dai ban cuceki ba."
Ganin Hajja tana nufo benan na fara cewa." Don zaka yi aure sai ka sanya ni a gaba kana zagin ubana, me ya yi maka?  Ina lefinsa da ya haife ni, ni ka zage ni mana amma ka daina ambato sunan mahaifina kana zagi ai bai nema a wurinka ba, a wurin Allah yake nema, wallahi Hajja na gaji ba zan iya ba." Na kàrasa maganar da kuka mai karfin gaske....

Hajja ta dube shi da mamaki a tare da ita ta. Kafin ma ta furta wata kalma anti Yagana da take ta jefo mini harara ta ce." To idan auran zai yi ai ba za ki hana shi ba, wane irin wulakanta kai ne wannan Amina." Hajja ta ce.'" A a Yagana a yi magana ta hankali mana, iyaye ai ba abin wasa ba ne, kina jin fa abinda ta fad'a."
"Wallahi tallahi idan duk jikina kunnene ba zan yarda da cewa ya zageta ba, Hajja na san halin kayata."
Hajja ta girgiza kai tana dubansa ta ce." Tajo ashe aure za ka yi ba labari."
Yar dariya ya yi  irin ta takaici  yana ko'karin cire rigarsa dake ri'ke a hannuna ya ce." Ban tashi yin ba dai kawai ta ji muna waya da Hauwa shine ta daga hankalinta.
Sai ta dube ni tana dan murmushi wanda na kasa tantance ko na menene ta ce." To ki yi hakuri kin ga kina tare da lalura, kishi a yanzu ba na ki ba ne, fatan mu dai ki sauka lafiya."
Sai na yi kasa'ke ina kallonta. Anti Yagana taja tsaki ta bar wurin na san haushina take ji kan abinda na yi.
Ganin haka sai shima ya silale Ina kallonsa ya sauka da saurin gaske. Hajja ta fara rarrashina akan na nutsu kada na daga hankalina tunda ai banga an yi ba.
Sai a lokacin kunya da nauyin matar suke kama ni. Idan na ce zan yi irin wannan dibar albarkar to zahiri zan bata kwa'bar da na yi.
Hakama ina shiga d'aki anti Yagana kamar ta dake ni  tana cewa. Wallahi kada ki bari ki kai mutanan nan karshe Amina, in banda rashin mutunci da samun wuri ina ruwanki da shiga lamarinsa da 'yan uwansa, idan auran ma yace zai yi menene abin damuwa, mutumin da bai tauyeki ba shine zaki tona masa asiri har da cikwukwuye masa riga saboda kawai kin ga suna sonki, ko

kuwa sa'anki, babba dashi irin haka, waye ya gaya miki yanzu ana irin wannan kishin na hauka, ba ki ta'ba ban haushi ba irin yau wallahi.
Na nemi gefan gado na zauna jikina a sabule hawaye na silalowa daga idona na ce." Anti Yagana zagina fa ya yi wai don ubana, ina ga duk rikicin da za mu yi dashi idan cin zarafin iyaye ya shigo sai inda karfina ya kare wallahi."

"Bango ki ka kaishi, ai tunda na zo gidan ina fuskantar irin zaman da kuke yi, wasu lukutan kamar kece kike auransa abinda kika ce shi za a yi, dama ai mai ha'kuri bai iya fushi ba.
Na ja hanci raina na cigaba da suya domin na gama fahimtar cewa anti ba zata saurari uzuri na ba, kuma har yanzu ta kasa gane abinda nake ji a zuciyata game da maganar Hauwa. A dake ka kuma a hanaka kuka. na kwanta kusa da Hadiza da take ta bacci duk maganganunmu bai sai ta motsa ba, anti ta cigaba da maganganu tana fad'in. " Ina ce ba daga gidan kishiyoyi ki ka fito ba, Alhaji Muntari wannan bagidajen mutumin ba matansa biyu ba, kece fa ta uku kin san ba kya son kishiya me yasa ki ka aure shi, sai wannan saboda kin fahimci lagonsa akanki kike dabdala  a kansa. Wallahi ki ki yayi fushin irinsu, kuma idan ki ka ce ta irin wannan salon za ki dinga nuna kishinki zaki fice masa daga rai. Ko waye ya gaya miki anayi wa namiji irin haka ya cuceki idan zaki farka ki farka."
 Cikin kuka na ce." Anti Yagana don Allah ki kyaleni haka ba ki san abinda nake ji ba ne, shiyasa kike yi mini wannan maganganun lamarin bai zo kanki ba ne."
"To shikkenan ki yi mini rashin kunya don na gaya miki gaskiya ba sai kin kara ganina a gidan naki ba, duk abinda za ki yi, ki je ki yi rayuwarki ce, ke za a yi ta lissafawa aure, ace kowane d'a da ubansa."
Hawaye ya kara shararo mini shiru na yi mata ban sake cewa komai ba. Ita tunda ta ce haka ba ta sake wata maganar ba, ta fita falo wajen Hajja.

Ko'karin daure zuciyata na yi duk da abinda yana sasakata ban nuna ba ina so mu rabu lafiya don ganin yadda take ta jin haushina tana fushi da ni, na dinga bata ha'kuri har sai da huce tukkuna, na hada mata abubuwa masu yawa da kudi haka ma maigidan dubu dari biyu ya bata wai ta sayawa yara alawa.  Koda zata ta tafi kasa daurewa na yi kuka na dinga yi haik'an! kamar 'kan'kanuwar yarinya  Ita kam bata wani nuna alhini a zahiri ba amma dai na san cikin zuciyata tana jin rashin dadi. Ina kallo su Hadiza da Yusi suka tafi rakata filin jirgi, ni kuwa ya ce na zauna kawai a gidana. Haushinsa ya kara nauyi a zuciyata. Ita kanta Hajja sai da ta goge kwalla domin gaskiya sun shaku sosai da Anti Yagana.

 Duk yadda na so da na manta da abin kasawa na yi domin sai nake ganin kamar ni ya takewa hakki. Akwai cin fuska a cikin abinda ya yi mini, dalilin ma da ya sanya kenan na yanke shawarar akan ba zan sake lamunta yayi waya da wata mace a cikin gidan ba koda kuwa ma'aikatansa ne. Idan har yana so ya zauna da ni lafiya. Ni ba namijin da zan zauna ya zagi Ubana gobe kuma na washe masa baki wallahi sai na nuna masa kuskuransa ba

ruwana da kudi da shekarunsa iyaye ba abin wasa ba ne. Tare nake zaune da mahaifiyarsa ban ta'ba gaya mata bakar magana balle har na dubi tsabar idonsa na zageta. Ubana bai yi masa komai ba, ba kuma zan yarda ya saba da zaginsa ba ai kud'i ba hauka ba ne.

Sati biyu babu jituwa a tsakanina domin duk yadda ya so da ganin mun shirya naki bashi fuskar hakan. Gaisuwa ce kawai take hadamu idan na sako daga samansa ba na sake komawa sai wata safiyar  ina kula sosai domin kada Hajja ta fahimci akwai matsala a tsakaninmu.
Tun yana rarrashina har dai ya ha'kura ya zuba mini ido. Muka cigaba da zama a  hakan.  Ranar wata lahadi na tashi da ciwon kwankwaso domin tunda cikina ya shiga wata na bakwai nake jin sauye-sauye a tare da ni. ji nake yi kamar haihuwar fari don ba karamin wahala nake ci ba.
Da kyar na yi wanka na zura jallabiya wajejen takwas da kwata na nufi saman nasa.
Na same shi yana ta waya na zauna na yi kasa'ke ina sauraransa ya kammala ya dube ni. Uffan bai ce mini ba. Na turbune fuska da kyar na ce." Ina kwana.''
Ya yi mini shiru bai amsa ba."
Na ja hanci takaicinsa kamar ya kashe ni domin dai na fahimci da Hauwan yake magana da sassafe 'yar iska ko uban me take gaya masa oho."
Na ce." Wai me kake jira ne kai ba yaro ba haka zalika itama ba yarinya ba tsohuwar guzuma ce fa ko yau a d'aura muku aure sai muga k'aryar wayar sassafe."

Babu sukuni ya ce." Saurin me kike yi madam an kusa in sha Allahu rabbi."
Sai na ji kamar ya soka mini mashi a wuya. Na ja tsaki tare da kawar da kaina gefe."
Ya ce.'" Wai ke daman haka ki ke ne, ba ki da kunya?"
Shiru na yi ban ce masa komai ba."
Ya sake girgiza kai a karo na biyu ya furta." Ba tsoronki nake ji ba, kuma duk take takenki na gane wallahi ba zan rabu dake ba dan zan yi aure, kuma zan fito miki da asalin kalata tunda baki da mutunci."
Hawaye suka 'kwace mini na ce." Ni ce ma ba ni da mutunci ko? Wallahi idan kuwa kana son zama da ni cikin salama sai ka bi dokokina domin kuwa ba zan zauna ka dinga raina mini hankali ba. Ka zage ni ka zagi Ubana akan wane dalili. Ni bana asiri amma zan had'aka da Allah idan har rabuwarmu itace alheri Allah Ubangiji ya tursasaka ka ba ni takardata.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*

*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550

5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*17*
Ya dinga kallona kafin daga bisa ni ya ce." Na rasa wace irin macece Allah ya had'a ni da zama da ita. Ana ga gabas kina ga yamma An gaya miki kishi hauka ne, mahaifinki fa mata biyu gare shi, to ni me yasa zaki ce ba zan yi ba, ko kina yi mini bakinciki na samu abinda na rasa a baya ne."
Na ce.'" Na gaya maka duk abinda za mu yi kada ka sako mahaifina a ciki, shi ka raina ko? Kwanaki ka zage shi yanzu kuma kana so ka gaya masa magana. Akan wane dalili? Na rantse da zatin Allah ba zan jure hakan ba zan d'auki mataki."
Maganata sai ta bashi dariya ya dinga yi yana kallona daga bisani ya girgiza kansa yana fad'in." Ki d'auki duk matakin da za ki d'auka, ina jiranki, a dake dai ba zan daku ba, kuma ni sharri ki ka yi mini ba ta inda na ambaci sunan mahaifinki na zage shi, yarinyar nan har yanzu ba ki san wanene Tajo ba, amma Humm!"

Kada ki karanta littafin nan ba tare da kin biya ni hakkina ba yar uwata.

Tashi na yi na fita daga d'akin domin Ina ganin zamana ba zai haifar da d'a mai Ido ba. Da daddare misalin sha daya da wani abu ya kira ni a waya don har na kwanta ma muna hira da Hadiza kad'an kad'an bacci Yana fizgata yace na same shi a samansa. Ba na so Hadiza ta gane muna fad'a dashi na tashi nasa hijabina na fita.
Yana tsaya a bakin kofa ina shiga ya murza mukulli. Na dube shi babu fara'a."
Gani.'' Sai ya kamo hannuna ya ja ni muka nufi gado.
Tunda na ga taketakensa na fara janyewa domin ba na jin dad'in komai rayuwata a takure nake yin ta. Ga kuma takaicin da yake k'unsa mini.
Duk daburunsa suka kare jikinsa ya dinga kyarma, domin ya kai makura wajan bukatuwa kuma ya kasa samun hadin kaina. Duk inda ya ta'ba a jikina zan ce wayyo, ko na d'auki hannun na cillar dashi. Ya kasa sarrafa ni domin na cure wuri d'aya tamkar alkaki. Sai ga kwalla mai yawa a cikin kwarmin idonsa saura kiris ta zubo.
"Ki bari na yi ko kad'an ne a hankali zan yi na gaya miki, ba ni da wata iyalin sai ke, ki daure kada ki jefa ni a cikin matsala, Amina ke kanki kin san na yi juriya sati biyu ban nemeki ba ba na so na gwada miki karfi." Wad'annan maganganun yake furtawa jikinsa yana rawa yayin da gumi keta keto masa. Ya kai hannusa ya dora  a kirjina yana shafawa. Na cire da sauri na juya masa baya. Sai yake matso ni yana shashsheka." Kashe ni kike so ki yi ko? Me na yi miki ki ke shiga hakkina, kin san bala'in da nake ciki kuwa amina."

Shiru na yi masa don har yanzu bai fara ba ni tausayi ba.
"Okey ki gaya mini nawa zan saya tunda ba zaki ba ni nayi don Allah ba, na ce ki gaya mini nawa zan siya."
A hankali na ce." Ba na siyarwa ba ne.'"
Ya riko kafadata tare da dora fuskarsa a tawa Yana cewa.'' To na ji, ki bari ko ban shiga wannan wurin ba na yi wasa da wannan kin ji ko." Ya kara kai hannunsa kirjina. Na ture shi na tashi zaune tare da matsawa can karshen gado.
Ya tashi zaune shima na kalleshi gabad'aya duk ya firgice girmansa ya fito sosai. A ki'dime ya ce." Wallahi tallahi zan gwada miki rashin Imani yanzu. Ke wace irin muguwa ce ne? me na yi miki, ko ke yarinya ce karama?"
Shiru na yi masa ban tanka ba. Sai yanzu zuciyata ta fara sanyi domin ganin yadda na samu damar rama abinda ya yi mini."
Ya danna kafadata da k'arfi zai kwantar da ni. Na kuwa bude baki da k'arfi na tsala ihu! Ina fad'in." Wayyo cikina."
Ya cika ni da saurin gaske yana gyara mini cinyata data lan'kwashe. Na d'ora hannuna kan cikin ina hawaye. Shi ma ya kai hannunsa kan cikin daidai lokacin da yake ta motsi. Kusan minti biyar ya cire hannunsa. Ya lalubi gajeran wandonsa ya sanya.  Ina kallonsa ya sauka daga gadon kamar mara laka a jiki ya nufi bandaki, tsaki na ja na tashi zaune.

Tunda haka ta faru a tsakaninmu bai sake nema na a shimfida, bai kuma 'kullace ni ba. Ni din ce ma na tsiri gaba dashi duk da na san ta  wani gefan ya fi ni gaskiya  amma ban yarda na nuna masa ba, domin zahirin  gaskiya na ji ciwon zagin da ya yi mini.
Ban sake hawa samansa ba run ranar da abin ya faru sai na bari ya sauko tukkuna muke gaisawa, itama babu cikakkiyar sakewa a tsakaninmu Ita da kanta Hajjan ta fahimci akwai rashin jituwa a tsakaninmu. Wataran ta same ni a d'aki don kwana na yi ciwon mara ban kuma gayawa kowa ba ko ita Hadiza gajiya ta yi da tambayata ta rabu da ni.
Tana shigowa na yun'kura na tashi zaune Ina dan yamutsa fuskata. Ta zauna kusa da ni muna kallon juna na sake gaisheta duk da cewa da safe mun gaisa. Hadiza dake gyara kayanta a kwati itama ta sake gaisheta. Sai ta ce." Yau na ji ku shiru baku fito ba har ke Hadiza tun bayan da muka gaisa da safe na ce yau ba kwa jin hirar ne."
Hadiza ta ce." Wallahi ni na tsaya gyaran kayana ne Hajja ni ma yanzu nan nake zancen a zuciyata.
Sai ta dube ni a nutse ta furta." Ai na d'auka ko wani abin aka yi muku."

Yar dariya na yi gyara zama na ce." Hajja waye zai yi mana abu kuma, na d'an tashi da ciwon jiki ne wallahi shiyasa ban fito ba."
Cikin nazari irin na manya ta ce." Ai wannan ya zama dole tunda kina kan ga'ba, amma dai na fahimci akwai damuwa a tare dake tsakaninki da mijinki akwai matsala ko Amina?"
Girgiza kaina na yi da sauri na ce.'' Babu wata matsala Hajja me ki ka gani?"

Ta ce." Na ga abubuwa da yawa  a cikin satin nan to na yi miki uzuri ne dalilin lalurar dake tare dake ni kaina ba na son abinda zai daga miki hankali."

Shiru na yi ban ce komai ba, amma maganarta kamar ta famo mini abinda yake damuna. Kwalla mai zafi ta zubo mini."
Ta dubi ni tana girgiza kanta ta ce." Maganar Hauwa tana damunki Amina, me zai sanya ki tashi hankalinki akan abinda ba ki ga an yi ba."

Na yi shiru ban ce mata komai ba, don gaskiya ina jin nauyinta sosai. To ya zan yi ne na yi kokarin ganin na danne abin a raina smma ya faskara ni kaina ban san ina da zafin kishi ba sai akan d'anta.
Ta riko hannunawana a nutse ta furta." Kada lamarin Hauwa ya daga miki hankali Amina, ni ina son tarayyarki da Tajo, kuma muddin ina raye ba zan bari ki wulakanta ba, kada ki ga Hauwa 'yar uwasa ce ki sanya a ranki cewa ko ya aureta zaki wula'kanta ko d'aya. Dake da ita duk daya kuke a wurina. Tajo ko bai  auri Hauwa ba ai ba mu isa mu hana shi auran wata ba tunda Allah ne ya halasta masa, kada ki bari ya fahimci gazawarki ta wannan gefan kin ji ko."

Hawaye masu rad'adi suka fara ambaliya a fuskata kuka nake sosai domin yanzu na sake gazgata lamarin tunda gashi mahaifiyarsa tana gaya mini akwai fa auran  ko mu dade ko mu jima, to ya zanyi da tsananin tashin hankalin da yake yun'kuro mini a zuciyata. dama wai haka ake kishin, ni fa tsakani da Allah ban ji kishi ko kad'an ba a lokacin da nake tare da Alhaji Muntari. Ban san yadda aka yi  nake masifar tsanar na ji ana danganta shi da Hauwa ba sai duk hankalina ya tashi.
Rarrashina sosai ta yi  da kalamai tausasa don ba ta fita daga d'akin ba sai da ta tabbatar na sake na daina kuka sannan ta fita da zummar yin sallar la'asar.

Hadiza ta dube ni tana tabe bakinta ta ce." Aure ko shekara ba a yi ba zai miki kishiya to ke yanzu haka za ki zauna babu wani taimako da za a yi mini. Ni fa wallahi ban yarda da Inna Uwani nan ba, gani nake kamar da sanya hannunta wurin sanya miki tsana da kiyayyar mijinki har ma da zafin zuciyar da kike ciki.

Kallonta na yi ina auna maganarta. Idan na fahimci inda ta dosa tana so na bi malamai da zummar a taimaka mini kada mijina ya yi aure ko kada na yi boranci a gidan
Ban iya ba tun farko kuma ba zan yi ba a yanzu, dama ita da Ummansu ne suke yi babu wanda bai sani ba dan shi kansa Babanmu ha'kura ya yi, ya kyale su amma ana yawan kawo masa tsegumi anga Ummansu tana binne laya a gidan tururuwa.

Na ce." Hadiza zan nemi taimakon Allah kawai, amma kada ki kara yi mini maganar na nemi taimako a wurin wani asararre me zai yi mini banda ya

kara dagula mini lissafi.  Kin ga a yanzu wallahi ji nake yi ina ma mutumin nan ya sake ni na huta don mugun haushinsa nake ji."
Ta ce." Kin ji ko, ai na gaya mini farrak'u ake so a yi muku shiyasa ma aka dasa miki kiyayyarsa, in banda haka menene abin kyama, ai idan ni ce nake cikin wannan daular wallahi ba zan wani damu ba don zai yi aure zan bi ta karkashin kasa ne na ruguza shirin.

Tsaki na yi, na yun'kura na tashi domin daura alwala ganin lokaci yana kurewa. Har na fito daga bandaki ba ta daina mita ba, wai mamaki take yi na ce ina so na bar gidan.
Cikin zuciyata na ce dama ke ai duniya ki ka sanya a gaba.

Ko kusa ko alama ban ta'ba kawowa cewa Inna Uwani za ta shiga tsakanina da mijina ta hanyar asiri ba. Na dai fi tunanin shi din ta yi masa asirin da zai auri 'yarta tunda na lura hakan shine burinta.

Nasiha da jan hankalin da Hajja ta yi mini sun dan taimaka wurin sassautowa ta, amma dai duk sanda zan kalleshi sai na ji zafinsa a zuciyata.
A ranar kuma don na nuna mata cewa na d'auki maganarta a gabanta na bi shi saman bayan ya shigo gidan. Hakan kuwa ya yi mata dadi sosai don  a jikina na ji ta bi ni da kallo a lokacin da nake da niyyar tafiya d'akin nasa.

Tabbas da na san kunnuwa za su ji mini abinda zai daga mini hankali da ban bi shi ba. Ban ta'ba tabbatarwa da kaina namiji karin maganar nan gaskiya ne sai yau inda hausawa suke cewa namiji kanin ajali ne. Yau na gazgata domin ina shiga d'akin kunnuwa suka ji maganar da yake yi a waya mai tayar da hankali.
Yana tsaye a tsakiyar d'akin ya juya baya tunda dama kofar a bud'e ya barta dalilin ma da ya sanya kenan bai ji shigowata ba. Wayarsa yake hankalina kwance yana ta dariya kamar bashi da damuwa cikin annashuwa yake fad'in." Waye ya gaya miki ni mijin tace ne? umm! Ai ba haifi macan da zata juya ni ba Hauwa, idan kin ga na bar abu ni na so, ita kanta matata tana da alfarma ne a wurina shiyasa kuke ganin kamar ina tsoranta, ta aure ni a lokacin da kowa yake gudana, sannan ta daraja mahaifiyata a lokacin da ta nemi alfarma a wurinta. wannan abu biyun sune suke ri'ke da ita a gidana. Ina kuma jin zan iya cigaba da zama da ita dalilinsu, amma ke kanki kin san irin ra'ayina, ba kasafai na fiye son mace mai jiki ba. Ina ganin yanayinki da Samira ya kara jan hankalina gare ki Hauwa....✍
TAB! NAMIJI KENAN.
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*

*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950

3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*18*
Ban ji mai ta gaya masa ba tunda ba hands free ya sanya ba. Na dai ji yana fad'in." Ok, ok babu damuwa, nawa ne kudin gyaran jikin?"
Ya yi jim kafin ya ce." Idan na yi wanka zuwa an jima zan saka miki, amma kada ki tsammaci d'aurin auranmu nan kusa kamar yadda na gaya miki, mu bari ta haihu tukkuna sai a yi komai a tsanake."
Ya sake yin jim kafin ya ce." Ok my love I miss you."
Ina tsaye har ya kammala yana juyowa muka had'a ido. ya dan razana da ganina tunda ya san na fi sati uku rabon dana tako kafata dakinsa. Cikin kankanin lokaci ya daidaita yanayinsa bai ce mini komai ba ya nufi bandaki. Na tare shi da hanzari muka tsirawa juna Ido.
Cikin zafin kishi dan har wani garara-garara nake gani a idona ce." Don girman Allah da Annabin rahama daga yau na daina cin arzikin da nake ci a gidanka sai me don ka kwance mini zani a kasuwa, ka gayawa wadda zaka aura ga yadda aka yi auranmu. Ai sun sani ita da babarta ba sai ka jadadda mata ba, baka tona mini asiri ba wallahi kanka ka tozarta ba ni ba, a yau ina gaya maka na yi nadamar wannan cikin na jikina, domin dama da dole aka yi mini."
Bai ce mini komai ba ya ratse ni zai wuce. Na ri'ko rigarsa ta baya da karfin da ni ban san ma ina dashi ba."
"Ai ba zaka burge ni ba sai ka auro kaf siraran duniya sannan za ka burge ni, kuma daga yau na daina cin arziki wata idan ka isa ka haifu ka sake ni na ce maka."

Fuzge rigarsa ya yi yana nuna ni da yatsansa." Na gaya miki ki shiga taitayinki fa, an fad'a din kina cin alfarma, ki yi abinda za ki yi."
Wasu hawaye suke keto kumatuna suka fara kasa tsare......'Abinda zaka ce kenan ko? to Allah Ya isa ban yafe ba maka."
Ya rike 'kugu kamar mace yana dubana ya furta." Da na yi me? ai idan Allah ya isa ne, ni zan yi miki, haka kawai kina nema ki jefa ni cikin matsala, idan auran ne ma ai kece ki ka asassa mini yinsa, kuma na gaji da abinda ki ke yi mini zan kira mahaifinki na gaya masa ko na kira antinki Yagana ba zan iya da bakin hali irin naki ba Amina na gaji da rarrashinki domin ni ba bawanki ba ne, haba duk ga mata nan birjik a gari ko kina ganin ba zan iya rabuwa dake ba ne?" Kasa magana na yi domin jin wani irin jiri na kokarin zubar da ni a wurin. Ya shige bandaki ya bar ni a tsaye duk dauriyar da nake yi sai da hawaye ya zuba.

Ina nan tsaye kamar dasashen itace ya fito ya same ni a inda ya barni, ya dube ni da mamaki a fuskarsa amma bai ce mini komai ba ya nufi wurin kayan shafarsa. Yana shafa mai a jikinsa amma gabad'aya hankalinsa yana kaina, ina kallon duk wani motsinsa ta gefan idona. Yanda ya nuna a shirye yake da tarar duk abinda nake ji dashi.

Ban ce masa komai ba na kad'a kaina na kama hanyar fita daga d'akin ina goge hawayen da yake zuba amma ya'ki tsayuwa idan na tuna abinda ya gayawa Hauwa akaina sai zuciyata ta d'auki zafi mai tsananin gaske. Ashe soyayyar karya yake yi mini domin ya amfana da jikina ne, babu irin kalamin soyayyar da baya yi mini idan muna kwance a bargo guda. Wai ashe akwai ranar da zata zo ya ci mini fuska a wurin matar da yake shirin aurowa.
Cikin damuwa mai yawa na sauka kasa, kuma duk yadda na so da ganin na daidaita kaina abin ya gagara domin zuciyata ta gama karyewa da mutumin nan munafiki ne na karshen, gashi ya riga ya gama da ni tunda ya d'irka mini ciki ya san dole wasu kudirorin nawa na janye su.

Hajja hankalinta ya tashi ganin yadda na sakko a hargitse ta kama ni ta zaunar kusa da ita. Lokacin zuciyata ta sake tsinkewa hawayen ya tsananta zuba a kumatuna.
Cikin damuwa ta fara tambayata abinda ya faru, gabad'aya yanayinta ya canza, sai na ji tsoron tashin ciwonta domin jikinta sai karkarwa yake yi. Ta dinga fad'a tana fad'in na gaya mata abinda ya yi mini.
Na yi kokarin tsayar da kukan da nake yi a raunane na ce. " Hajja ni ba zan hana shi aure ba, amma don Allah ki yi masa magana ya daina kwance mini zani a wurin wadda zai aura da kunnena na ji yana gaya mata cewa ina zaune a gidansa ne a matsayin alfarma, amma bana daga cikin irin kalar matan da yake da burin aura.
Hajja kin fi karfin komai a wurina a yanzu dai ko kara ki ka ajiye ki ka ce kada na tsallaka zan kiyaye saboda irin kulawa da soyayyar da kike mini, amma kalamansa suna nufin haddasa husuma tsakanina da Hauwa idan Allah ya kaddara shigowarta gidan nan, kin ga dama ya gaya mata ga yadda akayi ya aureni ai ba zata mutuntani ba tunda alfarma ya yi mini. Sannan tunda maganar auran nan ta b'ullo yake gaya mini duk maganar da yaga dama harda zagin iyaye Hajja ba zan iya jurewa ba domin iyaye sun wuce raini."

Ta dinga girgiza kanta tana fad'in." Alfarma ai ke ce ki ka yi masa Amina, kuma dole ace da mijin iya baba. Duk inda za a je kece Amina dai da ki ka aure shi a lokacin da kowacce mace ke gudun rab'ar inda yake ba don komai ba sai dan saboda matsalar da take tattare dashi.
Ke alheri ce a wurinsa shine bai sani ba da har yake fad'in wad'annan maganganun kuma wallahi muddin ya ce zai biyo ta irin wannan sigar zan rusa maganar auran gabad'aya."
Tana rufe bakinta ya sauko cikin jallabiya da wayoyinsa hannu. Ya zauna yana kallonmu wani irin yanayi a tare da shi.

Aikuwa ta rufe shi da fad'a ta inda take shiga ba ta nan take fita. " Wallahi Tajo ka kiyayi 'batawa matarka rai, kai baka da tausayi ne, baka duban abinda take d'auke shi kullum cikin daga mata hankali kake kana sanyata koke-koke. wai har kana cewa zaman alfarma take yi a gidanka. To idan har Amina zaman alfarma take yi, ni ma alfarma kake yi mini, yanzu ba ka ji kunyar yi wa yarinyar nan haka ba, kada fa ka manta tilasta mata na yi rana daya ban ta'ba ganintaba, itama bata taba ganina ba, amma saboda mai biyayya ce ta amince har ta aureka bayan duk ta san abinda yake faruwa da rayuwarka. Me yasa a lokacin da muka nemi Hauwan ta maye gurbin 'yar'uwarta taki amincewa saboda tana tsoron mutuwa, amma ita Amina ta sadaukar da rayuwarta ko ta mutu ko ta yi rai bayan tana da tarin k'udurori a rayuwarta. Tajo ba kai ka yi wa Amina alfarma ba, itace tayi maka alfarma ka ajiye hakan a cikin ranka, kuma muddin kana son mu zauna lafiya da kai ka kiyayi 'bata mata rai."

Sai da ya bari ta gama fad'an tukkuna ya sassauta murya a nutse ya ce." Hajja ku yi hakuri don Allah, amma yana da kyau ki saurari uzurina a wannan ga'bar ina da abubuwan da suke damuna game da yarinyar nan. Dalilin da ya sanya ban zo na gaya miki ba saboda naga ita din mafi soyuwa ce a wurinki, amma ai ni ma tana kwarata kwarai da gaske gashi bata da kunya wallahi, bata ganin girma da shekaruna kamar sa'anta haka take sa'insa da ni. Sannan bata ba ni kulawa ta kowane bangare, ta hana ni hakkina tsayin satika, kuma ina cikin sha'awa, duk lokacin da ki ka ga ta hau sama wajena wallahi masifa ta je nema ba kwanciyar hankali ba, ni duk yadda na so mu zauna lafiya ta'ki, yau ta ce wannan gobe ta ce wannan, ta'ki ta bari mu fahimci juna."

"Ayyo, shiyasa kenan kake sanar da Hauwa ta shigo a shirye itace matar so ko? gata 'yar uwarka, ga shi kuma kana sonta saboda tana kama da Samira, sannan siririya ce ita Amina kuma 'yar lukutan, sannan ni ce nace ka aureta, ni da ita muna cikin alfarma."

Murmushi ya d'anyi ya saci kallona. Ina ta goge hawaye don na ji dadin titsiyar da Hajjan ta yi masa, na cigaba da jan majina Ina shassheka da sake nuna raunina don kada ta yarda da abinda ya gaya mata a kaina.

Ya ce." Ni wallahi ina sonta Hajja ban ma san irin kalar son da nake mata ba, itama damar da ta samu kenan take yi mini iyashege yadda ranta yake so, ki daina fad'in tana cin alfarmar nan Hajja.".

Ta ce."To ai ba zata yi maka karya ba tunda dai da kunanta ta ji kana gayawa kishiyarta baka sonta ni na aura maka ita.
Da sauri ya ce." 'Karya take yi wallahi ni yaushe rabona ma da na yi waya da Hauwa, ni fa auranta bai wani kwanta mini a rai ba Hajja saboda k'arfafa zumuncinku da inna Uwani ya sanya har nake bibiyar maganar."

Da sauri na dube shi jin yadda yake rantsuwa da wallahi bai yi magana da Hauwa ba.
Hajjan ta ce." Oho toni dai na gaya maka ka kiyayi b'atawa matarka rai, ba wai dan za ka yi aure ka k'untata mata ba." Yadda take yi masa fad'a sai ka d'auka karamin yaro ne, shiyasa aka ce namiji duk shekarunsa a gaban iyayensa yaro suke kallonsa. Abin har ya d'an so ya ba ni kunya. Duk abinda ta ce masa a kaina sai ya ce to, babu musu da jayayya. Sai da ta kammala tsaf tukkuna ya nisa kafin ya ce." An gama Hajja, za a kiyaye in sha Allahu amma itama wane irin jan hankali za ki yi mata a game da irin abinda take yi mini."
Ta dube ni cike da tausayi. Ni kuwa na sake karyar da kaina ina d'an sake jan majina. Ta juya tana kallonsa kafin ta ce." Kai Tajo mace mai wannan lalurar ai abar tausayi ce wallahi kuma cikin nan wahala yake bata da gasken gaske, ai dan kai namiji ne baka san ya abin yake ba."
Ya kalleni babu yabo ba fallasa ya furta." Ni kaina abinda nake dubawa kenan Hajja shiyasa nake tausaya mata, amma itafa ba yarinya ba ce, duk dabarun da za ta yi mini na samu na nutsu ta sani, me yasa ba zata yi mini ba."
Hajja ta kawar da kanta ba tace masa komai ba, dan yadda ta nuna ma sam bata san maganar.
Ya sake rauntar da muryarsa yana cewa." Tana da taurin kai da tsayayayya Hajja, kuma bata tausaya mini irin na miji da mata ."
Ta dube shi hankalinta a kwance . " Baka ji tausayinta ba yaushe zataji naka, ai kai baka iya rarrashi ba, mace tsohon ciki ai abar lallabawa ce."
Ganin duk hanyar da ya bullo dan ta duba kokensa taki sai kawai ya fito mata a mutum ya cire kunya yana cewa." Ko yanzu abinda ya had'a ni da ita kenan, na nemata taki yarda, kuma wallahi tallahi a bukace nake Hajja, yarinyar nan ce halalina."
Kunya mai 'karfi ta rufe ni, da sauri na sunkuyar da kaina, ban kara kallon inda hajjan take zaune ba, dan ji nake yi maka kamar na tashi daga wajan.
Itama cikin jin nauyi ta yun'kura domin ta bar wajan tana cewa." Ni dai na gaya maka kada yarinyar nan ta sake kukan takaicinka, ai namiji kake duk hanyar da zaka bi wurin tausar zuciyata ta yi maka dabaru ka sani, kaine ka tunzurata har hakan ta faru a tsakaninku sai ka rarrasheta."
Tana gama maganarta ta bar wajan. Ni ma na fara ko'karin tashi ya cimma ni, ya zauna kusa da ni har jikinmu yana haduwa.
Sosai ya tausasa murya yana ce wa." Hajja ta dawo da soyayyar da take mini kanki Amina, kiri kiri sai ki yi mini laifi amma a nuna ni ne mara gaskiya."
Uffan ban ce masa ba. Ya kama hannuna ya rike a hankali ya furta." Kin san wani abu." Na yi shiru ban tanka masa ba
Ya ja numfashi tare da rintse hannuwana acikin nasa." Na yi kuskure akan abinda na yi, ki yi hakuri ki ajiye hakan a matsayin ajizanci irin na dan Adam zan kiyaye."

Gudun aure na kudi ne kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Kallonsa na yi Ina sake tuna lokacin da yake waya da Hauwa. Na ce." Wallahi ba zan yarda ba ai ba a cizan mumini a rami d'aya. Akwai manufar da ta sanya kake zaune da ni kamar yadda ka fad'a."

Ya jim yana kallon kasan kafet kafin ya ce." Ni dan Adam ne fa, dole a cikin ayyukana akan samu kuskure smma wallahi ban gayawa Hauwa hakan dan na tozarta ki ba, ina sonki kwarai da gaske."

Ta'be bakina na yi ban ce masa komai  ba domin gabad'aya na dawo daga rakiyarsa, mayaudaran kalamansa sun daina kayatar da ni.
Ya matsoni sosai yana fad'in." Me zan yi miki ki yarda da ni, my love umm dina!"
Na ce." Ba abinda za ka yi mini na yarda dakai Yallabai."
Na dafa kujera zan tashi ya kama ni ya rike sosai Yana fad'in." Bari na d'auke ki." Ban hana shi ba dani da cikin ya ciccibe mu gabad'aya a maimakon ya nufi d'akina sai ya yi hanyar samansa yana ta kallon fuskata.
Na bata fuska tare da cewa." Ka sauke ni."
Girgiza kansa ya yi Yana fad'in." Yau kome zai ki yi ba zan barki ba Amina, gwara ma ki nutsu mu yi abin nan cikin nutsuwa. Ba zan nemi matan wajan ba bayan ina da halalina a gida."
Na kawar da kaina ban ce masa komai. Ya dire ni a kasa ya bude d'akin cikin nutsuwa ya riko hannuna muka shiga d'akin.
Na zauna kan gado domin ji yadda marata take murdawa. Shi kuwa ganin ban yi turjiya ba ya kara masa kwarin guiwa, ya cire jallabiyar jikinsa ya rage daga shi sai gajeran wando ya zauna gefana a hankali yana kamo ni ya kwantar a kirjinsa.
Na tashi zaune da sauri. Ya tashi shima yana fad'in." Menene kuma?"
Na yi shiru ban ce komai ba.
Ya sake kwantar da ni a kirjinsa a karo na biyu. Na sake tashi zaune na zauna daram da ni. Don babu wani feeling da nake ji a yanzu sakamakon halin da nake ciki. Wanda na san da da ne, sai na fi shi kid'imewa. Daga zarar jikinmu ya hadu nake rasa gane inda kaina yake, amma yanzu  ba na jin komai ba.
Ya dinga kallona kamar zai rusa ihu!
Cikin rashin tausayi ni ma nake dubansa. Ya firgice ainun yayin da girmansa ya kara tumbatsa tabbacin a bukace yake kwarai da aniya.
Kafin na yi aune sai ganin hawaye na yi d'is ya d'iso a kumatunsa. Hawayen kuma a Ido daya.
Kamar na fashe da dariya haka na ji zuciyata wasai! amma ban nuna masa murnata a zahiri ba, na sake d'aure fuskata ina kallon gefe.
Ya dora hannunsa a cinyata wanda nake ta jin yadda yake ta karkarwa. A sarke ya ce." Kin ji."
Na dube shi sai na ga hawayen dai a idona daya ne yake d'isowa daya idon 'kemagadas! Cikin zuciyata na ce." baka daku ba tunda kukan da ido daya kake yi.

Ya sake furta." Kin ji."  Na ce." Me na ji?" Ya d'auki hannuna ya d'ora a jikinsa a kasalace da wata irin murya" Ki duba halin da nake ciki zan iya rasuwa na rantse miki da girman Allah gaf nake dana rasa rayuwata."

"Uhm!" Kawai na ce, na juyar da fuskata. Sai ya matsoni  sosai yana zira hannunsa a rigata. Ban hana shi ba, ya samu kirjinna sosai ya had'asu da hannunsa daya ya dinga luguda yana sakin nishi.
Na yi masa shiru don ko motsi ban yi ba, amma sa'kon ya dan fara shigata dalili ta hanyar nan ne kawai ake iya kamo sha'awata.
A hankali ya kwantar da ni, ya cire rigar jikina kamar yana lallaba 'kwai ya mikar mini da kafafuna ya kwance zanin dake daure a kuguna.
Na yi gim! abuna domin yadda yake motsani da tattaba naman jikina sai nake jin kamar tausa yake yi mini.
Abin bai tsaya iya nan ba yau harda lashe lashe ya dinga yi. Yana hadawa da d'an cizo irin na fatar lebe.
Cikin shagwaba da son bijirewa na ce." Me na yi maka kake cizona."
Ya cire bakinsa dake kasan marata ya dawo dashi fuskata a nutse ya ce." Ban cijeki ba my love dina." Ya kare da jan wani irin nishi, wanda ya jefa ni cikin wani yanayi. bakinsa ya sanya a wuyana ya dinga sid'a
yana lashewa. Yadda na fahimta guru-gurun da yake wuyana yana mutukar rud'ar dashi. Lokaci kan'kani sha'awata ta motsa wanda a da nake tunanin ta tafi gabad'aya dalilin cikin jikina. Ban san lokacin dana tallafe masa kai ba, a hankali na fara shafa saisayayyar sumar kansa tare da fuskarsa ina dan zira karamin yatsana a kunnansa. Haba sai lambarin ya kara tumbatsa. Ya fara fito da ainihin abinda ya assasa mini mugun kishinsa a k'ahon zuciyata. Wata irin  soyayya da salon sace zuciyar duk wata 'ya mace ya shiga gwada mini, wanda har sai da na fashe masa da kuka ina ma'kalk'aleshi sosai a jikina...✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k ne akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai

magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*19*

To had'uwarmu ta wannan rana ita ta kawo k'arshen rikicin da yake a tsakaninmu. Kuma tun daga ranar bai sake yin abinda zai janyo mana samun

sa'bani ba, yana kiyayewa kwarai da gaske amma dai maganar auran Hauwan tana nan haihuwata ta dakatar da shirye shiryen d'aurin auran. Ganin hakan ya sanya ni ma na sautata amma duk sanda na kalle shi sai na tuna abinda ya gayawa Hauwa akaina. Ina danne abin ne kawai domin a zauna lafiya, amma har yanzu naki yarda da maganar ajizanci da ya fad'a, domin na gane irin mazan nan ne masu munafurci da gumawa mace takaici.

****

Ranar talata da daddare misalin biyu da wani abu ciwon nakud'a ya kama ni. Lamarin ba sabo ba ne a wajena dalilin da ya sanya ma kenan ina jin ciwon ya bambamta dana koyaushe na tabbatarwa da kaina cewa haihuwa ce. Daga ni sai Hadiza a d'akin domin tunda cikin ya shiga watannin haihuwarsa na yi 'kaura daga d'akin magidan dalilin hana ni sukuni da yake yi a wasu lokutan kamar bashi da Imani idan fitinarsa ta tashi mun dinga rigima kenan, karshe dai dole nake ha'kura ya yi cikin dabaru tunda cikin yana tare wasu abubuwan da dama.

Hadiza ba ta san haihuwa ba tunda bata taba yi ba. Salati da numfarfashina ya tashe ta zaune a firgice ta riko hannuna tana tambayata."

Na ce mata." E, haihuwa ce Hadiza, ki kira mini Hajja akan ga'ba nake."

Da sauri ta kama hanyar fita tana fad'in" bari na kira ta.

Na yun'kura na sauka daga gadon da kyar a daidai lokacin faya ta fashe kafata ta cije sai na yi saurin dafa bango na durk'usa a wurin. Dama can ba ni da doguwar nakuda minti talatin idan ta yi tsanani awa daya a haka na haifi su Kamalu.

Shigowarsu d'akin a tare ya yi daidai da lokacin da abinda yake ya cika ya fado cikin zanin dana rufa a jikina. Sai kukansa ya karad'e d'akin.

Hajja ta nufo ni da saurin gaske tana fad'in." Da gamo da kasawa, Allah mai yin yadda yaso, Amina dama haka kike haihuwa"

Ban iya ce mata komai ba, illa kiran sunan Allah da nake yi har dai mahaifar ta fado sai sannan na ji hankalina ya kwanta.

Hajja ta zakulo abinda aka haifa tana fad'in." Hadiza kawo mini reza da zare." Ta fara dibi dibi, na ce." Ki bude dorowar jikin madubi."

Da sauri ta je ta d'auko Hajja ita ta yi duk abinda ya kamata bakinta ya ki rufuwa fadi take na samu 'kawa gata nan tubarka masha Allah. Sai sannan na fahimci abinda na haifa macece farincikina ya tsananta dan lokacin da akayi mini scanning ban yarda ba ganin cikin Yusi ban haifi macan ba bayan Kuma da akayi scanning haka suka rubuta.

Hadiza ta taimakawa Hajja suka gyara wurin. Ni ma na kintsa jikina na dan ja gefe guda ina mika godiyata ga Allah da yanke mini wahala cikin sauki.

A daran na gasa jikina. Hajja ta yi wa babyn wanka ta shiryata tsaf sannan aka sanar da maigidan halin da ake ciki.

Ban ta'ba ganin zahirin farincikinsa ba kamar wannan rana a lokacin da ya d'auki babyn sai da ya dan zubar da hawaye kafin ya danne zuciyarsa ya dinga godiya ga Allah bisa abinda yake yi masa. Sai ya dubi Hajja ya dubi babyn ya ce" Ban taba riskar kaina a cikin farinciki ba kamar yau Hajja Ni ma na zama Baba."

Ita dai dariya kawai take yi tana fad'in." To ai babu abinda ya gagari Ubangiji Tajo.
A ranar ya yi mata hud'uba da Nana Aisha dalilin k'aunar mai sunan bisa irin gudumuwar da ta bawa Ma'aiki S.A.W.

Gari yana kara yin haske ya kira likitan da tunda na samu cikin take zuwa ta duba ni akan ta zo ta domin ta duba lafiyarmu ni da babyna kasancewa haihuwar gida ana samun matsala mabambamta."
Cikin ikon Allah ko da ta duba mu lafiya lau babu wata matsala, a lokacin Allah ya lullube mata abinda yake da kawai. Dangi da 'yan'uwa daga bangarena bangaransa suna ta bugo waya domin addu'a da fatan alheri mussaman abokananansa sun taya shi murna sosai a yayin da yake ta shirye-shiryen kayatattaciyar walima. Ni ma inata gayyatar mutane dan mun yi waya da Anti Yagana ta ce mini za su da yawansu daga maiduguri Sahura ma haka. Shi ma Yusi Yana nan yana ta gangamin gayyatar abokanansa da ya hadu da su anan din. Hajja kamar dama a bangaranta ba a cewa komai ba, dan idan naga yadda take zumudi har tausayi take ba ni, ta kasa zaune ta kasa tsaye. Hadiza itace mai kira mata mutanenta a waya, a kira wannan a gayawa a kira wannan a gayawa. Mutanan Bauchi ma su Inna Uwani suna kan hanyar zuwa.
A yau da ya kasance kwana biyar da haihuwa tun safe mai k'unshi ta zo ta yi mini ja da baki. Da daddare kuma na ajiye a raina sai na je gyaran gashi.
Nana sunan da muke Kiran babyn kenan tunda ubanta ya riga ya yi mata huduba da sunan tana wurin Hajja tana bacci dalilin da ya sanya ma kenan na saki jikina da yawa domin yarinyar ba mai yawan kuka ba ce sa'banin wasu jariran da suke hana iyayensu bacci, tana da ha'kuri sosai idan ta koka to tabbas yunwa take ji, sai ta yini tana bacci a bayan Hajja ko Hadiza.

Tun kafin su k'araso wurin da nake na jin yadda take ta tsala kuka.
Idona akan Hadiza da take ko'karin kwantota daga bayanta tana cewa." Ki sake bata nonon tasha wata'kila
bata koshi ba, kin ganta nan, ta ki bayan Hajja sai tsala ihu take yi, ni ma shine na gwada goyata ko zata yi bacci, ta ce bata san wannan ba. Hajja tace na kawo miki ita ta ki bata nono, amma dai naga ta dan bubbuga cikinta wai ko kumbura ya yi.
Na ce. Hadiza kin ga duka hannuwana a daure da lalle don Allah zo ki taimaka mini fito da nonon asa mata a baki."
Na dan gyara ta sanya mini ita a jiki, amma fir taki kamawa. A lokacin ne na ji jikinta zafi rad'au.
Na ce." Hadiza ba ki ji jikinta da zafi ba?"
Za ta yi magana kenan Hajja ta iso wajan tana fad'in." Ba ta daina kukan ba, ko cikinta ne yake ciwo ne. Ta miko fidarta tana fad'in. A bata ruwan d'umin nan ko cikin zai saki."
Na ce." Hajja ba na jin kumburin ciki ne zazzabi ne a jikina, Hadiza ri'ke ta na cire lallan nan."

Da sauri ta dauketa daga jikina, na cire lallan da ba'a jima da sanya shi ba, hankalina gabad'aya ya tashi.
A ki'dime ta ce." Kai Innalillahi! Hajja kin ga abinda take yi."
Na dago kaina a sukwane! wanda ya yi daidai da lokacin da Hajjan ta 'karbeta daga hannun Hadiza tana jijjigata.
Ban san lokacin da nake k'unshin kafata ba. Sai gani a tsaye ina ko'karin karbarta daga hannunta. A lokacin idonta ya kakkafe sai sandarewa take yi a hannun Hajjan na fashe da kuka mai sauti a razane na shiga d'aki na d'auko wayata dake saman madubi hannuna na kyarma na nemi lambar maigidan domin sanar dashi.
Shi ma ya shiga rud'u sosai. Yana tare da baki don tun wajan shida na safe ya fita, ya ce maza maza mu tafi babban asibitin yara.
Na kashe wayar tare da shiga toilet na wanke kafafuna na fito na zura hijab.
Lokacin Hajjan da Hadiza suna harabar gidan. Yusi sai kuka yake yi. Itama Hajjan tana yi. 'Kasimu daya daga cikin direbobinsa ya fito da mota da saurin gaske muka shiga dan Hadiza ko mayafi ma babu a jikinta sai da muka je asibitin tukkuna ta ankara.
Emagency muka nufa abinka da family din babban mutum motar da ta kai mu asibitin itace ta shaidawa ma'aikatan daga inda muke.
Kafin kiftawa da bismillah 'kwararrun likitoci sun rufu akanta..

To duk ko'karin da likitoci sukayi kan ceto rayuwar baby Nana hakansu bai cimma ruwa ba. To ai dama kud'ira da hukuncin yana wurin buwayi gagara misali. Allah Ya kaddara kwanaki biyar kacal za ta yi a doran duniya ta koma ga mahallicinta. Hausawa sukan ce an nuna kama.
Duk na'urori da suka daura mata suka kwance a sa'ilin da suka tabbatar da mutuwartata bayan da jininta ya kone tas sakamakon cutar nan ta sikila wanda uwa da uban basu san cewa su As da As ba ne, sai da hakan da bayyana a tare da abinda suka samu ta hanyar aure.
To shi dai Yallabai din kamar ya yi dan karamin hauka don koda ya zo asibiti lokacin an nannad'e gawar yarinyar kuka ya sanya sosai a ofis din babban likitin da shi ya yi ruwa da tsaki akan ganin an ceto rayuwarta hakan bai samu ba. Kamar ba babba ba, ko kuma wanda bai san mutuwa ba, ya dinga tsiyayar da hawaye wanda hakan ya kara karya lagon likitan ya dinga rarrashinsa tunda kowa ya san aikinsa ne yin hakan a matsayinsa na likita. Sai da ya tabbatar nutsuwa ta dan shige shi sannan ya tambayeshi ya akayi hakan ta faru domin yanzu kai ya waye kafin ayi aure ana yin gwajin genotype domin gujewa wahala da haihuwar yara masu d'auke da wannan gagarimin ciwon da yake kashe su farat daya.
Kasa yi masa bayani komai ya yi. Kawai ya kar'bi takardun sakamakon gwaje gwaje da akayi wa yarinyar ya zira a aljihu. Da kyar ya iya furta." Idan na samu nutsuwa zan tuntubeka da shawara.
Rungume da ita ya fito a kirjinsa. Yusi ya ki'dime ya ruga da gudu ya tare shi yana kuka. Yayin da Hajja take gefe a zaune dan lokacin da aka fadi mutuwar kafarta kasa tsayuwa ta yi ta silale ta zauna a dandagaryar kasan wajan tana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!

Ina kallon Hadiza ma tana share hawaye wani na zuba sai ri'ke hannuna take yi amma ta kasa ce mini komai, lallai ranar naka sai naka. A lokacin ni kasa cewa komai na yi kukan ma ban iya ba can kasan zuciyata dai Ina ta kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! amma ina jin yadda wani kutittiran abu ya zo ya tokare mini a kirji.
Ban kara tsunkewa ba sai lokacin da ya fito da gawar rungume a kirjinsa. Sai kawai wasu hawaye masu zafi suka fara silalowa suna sauka a kumatuna.
Muka tsirawa juna ido, domin kuwa mu kad'ai ne muka san irin artabun da aka sha kafin samuwar cikin. Ya k'araso wurin da muke idonsa jawur hakan ya ba ni tabbacin da da cewa kuka ka yi. Ban ga aibunsa domin duk yadda zan fasalata muku tsananin k'aunar da yake wa babyn ba zaku fahimta ba.
Ya tsuguna gaban Hajja dake tankwashe da kafa sai kace wadda take tsakar dakinta. Ya dan bude fuskar babyn ina dan kallonsu ta gefan Ido domin gabana buguwa kawai yake yi don sai nake ganin kamar zai gayawa Hajja bata mutu ba.
Na ga hawaye ya silalo daga idonsa a sha'ke ya furta." Hajja ta rasu da gaske, ina cikin wani yanayi wanda ba zan iya tantancewa ba ki taya ni da addu'a."
Hajja ta sanya gefan hijabinta ta goge hawayen idonta. A nutse ta sanya hannu taja tawol din ta rufe mata fuska tana cewa." Ka yi hakuri, haka Allah ya kaddara, ba mai nisan kwana ba ce, mu je gida kawai a suturta Allah Ya sa mai ceto ce."
Yasa hannu ya goge fuskars kafin ya lalabi gilashinsa dake cikin aljihu ya sakaye idonsa, sannan ya mike tsaye likitan da escorts d'insa tare da Yusi suka bi shi a baya.
To ni din na ma fi su karfin hali domin tunda a karin farko na ambaci Innalillahi wa'ina ilaihi! na ji kwarin guiwa don ban sare ba, na ajiye a raina cewa dama ba mai nisan kwana ba ce. Ni na taimakawa Hajja ta tashi na gyara mata takalmanta ta sanya muka nufi bakin motar da jama'a suka yanyameta....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k ne akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*

*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*

*07084653262 ko*

*08089965176*

*SIYAN NAGARI!!!!!!*

*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*20*

Mutuwar sai ta zama kamar ta wani babban mutum domin kuwa abokanansa da tun daga haihuwar ya sanar musu sune suka dinga turereniyar zuwar masa gaisuwa da jajantawa cikinsu kuwa harda manyan mutanan da sukayi masa angonci ranar d'aurin auranmu a saudiya.
Ni da Hajja gayyar da muka yi sai ta zama ta zaman makoki don gidan cika ya yi da jama'a na kusa dana nesa. Dangin Mamanmu zugarsu guda daga maiduguri suka zo bisa jagorancin Anti Yagana washe garin ranar da suka tafi 'yan gidanmu suka zo kaf dinsu har da Babanmu da Baba Sule da wasu daga cikin yaransa. Da yake akwai sassa daban daban a gidan a can mazan suka taru, matan kuma muna tare tunda akwai d'akuna kusan shida a falon... Maigidan ya bada kwangilar yi musu abinci mai kyau daga restaurant. Domin ba mu da mai aiki mace dama falalu ne yake yi mana a wasu lukutan kuma ni ma na kan dan shiga kicin sai da cikina ya tsufa tukkuna na tafi hutu. Amma dai har yanzun Falalun shine yake yi ma harda Hajja. Inna Uwani ba ta zo ba amma ta kira suka kan hanya ta d'an yi jiyya ne amma ta warware a yadda take gayawa 'yar uwatata.
Satinsu daya suka shirya tafiya duk yawansu maigidan ya sanya direba yin jigalarsu a irin manyan bos din da yake da yake ajiye dasu saboda faruwar irin haka.
To gaskiya 'yan uwa sun nuna mini kara da alhini dangane da abinda ya sameni. Kowa da irin nasihar da yake yi da kawo mini misalai kan cewa duk wanda ya yi rashin dansa yana karamin yaro ana sa ran zai samu cetonsa a ranar alkiyama, Kuma na godewa Allah tunda ina da wasu ba ita kadai ba ce. Koda anti Yagana da Falmata suke yi mini wannan tsokacin a lokacin kasa tsayar da hawaye na yi domin ba kaina nake tausayawa ba maigidan ne abin tausayi domin daga randa akayi mutuwar zuwa yau ya kasa nutsuwa yakan 'boye kansa ya yi kuka abin ya yi ta ba ni mamaki, sai nake ganin a matsayin shekarunsa ya ci a ce ya ha'kura ya barwa Allah domin ita mutuwa rigar kowace, shi mai yi wa wani fad'ane amma shi yake yi, ya dora hotonta a fuskar wayarsa, na ce masa ya cire ya'ki cire hakan kuma da ya yi ba shi zai kawo masa nutsuwa da kwanciyar hankali ba.
Ni kam duk da abin yana sasakata hakan nan na barwa Allah na yi ciwon nono kamar me ya gaji da tsiyaya da kumburinsa ya sace. Daga zarar ta fado mini zan ta nanata Innalillahi wa'ina ilaihi! har na samu rangwami. Sai ya zamana shi da Yusi ne suke neman daga mana hankali a gidan. Shi ma Yusi ha'kuri kullum cikin zancenta da yake akwai sauran hankali har tambayar Hajja yake yi a can lahira wacece zata zama mamanta.
Hajja ta bashi amsa da cewa." Uwar muminai itace Maman duk wani jinjiri mace ko namiji da ya mutu Nana Aisha matar manzon Allah RT.
Duk wannan misalin da take kawo masa hakan bai sanya ya barwa Allah ba. Kamar yadda Baban nasa yake k'unshe kansa ya yi kuka Shima haka yake b'uya a koridon gidan ko cikin d'aki ya yi ta kuka.
Na same shi watarana yana yi na dinga yi masa fad'a domin hankalina tashi yake yi nima, ni na haifi abata amma na danne na ha'kura na barwa Allah ikonsa a ganina kowama sai ya ha'kura.

Fad'an da nake yi masa ya janyo hankalin Hajja da Hadiza da suke falo. Yaron ya fita ya barni ni kad'an a d'akin yana kuka. Na bishi falon ina cigaba da nuna masa illar hakan.
Yau kusan sati uku ya ci ace a ha'kura hakan. Hajjan ta ce." To sai a hankali ai Amina kowa zai manta kuma kin san zuciya kowa da irin tasa, Wani yana dauriya da juriya, wani kuma bashi da ita, bayan haka ma yarinyar dai ta shiga zukatan kowa kafin a manta sai an yara."
Na ce." Hakane Hajja amma ni idan naga suna haka sake dawo mini da lamarin baya suke yi. Shima fa Baba da yake wasu lukutan da haka nake kiransa na sha kama shi a dakinsa yana kuka kamar karamin yaro na yi masa magana ya'ki ya daina.
Ta yi murmushi tana cewa." Rabu da wannan Amina Inaga sai an had'a masa da rubutu, domin ni ma sai dare ya tsala ina bacci sai shigo mini idan na tambayeshi sai ya ce wai ya kasa bacci da ya rufe ido zai ga Nana ko da Samira ta rasu haka ya dinga yi mini wallahi sai a hankali kuma ya manta.

Shiru na yi ban ce komai ba na zauna saman kujera wanda ya yi daidai da lokacin da ya sauko daga samansa hannunsa ri'ke da manyan hotona irin na bango uku. Na yi mamaki sosai tunda a dan zaman da na yi dashi na fahimci bai fiye son bidia ba, domin kuwa yan alhalussuna basu yarda da kafe hoto a d'aki ba. Na farko ya ajiye frem din da yake d'auke da hoton tsohuwar matarsa Samira sai kuma ga hotonan baby Nana ya sanya a buda masa su lallai koda yana da wannan akidar ba ta yi tsanani ba tukkuna
Na bishi da kallo a lokacin da yake ko'karin isowa wajan da muke rungume da allon hoton nan dana tabbatar da cewa na Baby Nana ne, domin kuwa da kunnena na ji lokacin da yake waya yana bada umarnin yadda za a yi masa bayan ya turawa mai aikin hoton nata wanda ya d'auketa tun tana raye a wayarsa.
Kusurwa uku duk ya bi ya sa'kale allon hoton yarinyar ta fito sosai kuma ta yi kyau. Na tsirawa fuskarta ido Ina sake tabbatar da kamaninta da ubanta wanda a lokacin da take raye ban ga hakan ba duk kuwa da fadar da jama'a suke yi ban tabbatar ba sai yanzu da bata raye a duniyar.
Hajja ta dube shi tana fad'in." An ya Tajo ka so ka zauna lafiya kuwa, ka dubeka duk ka zabge lokaci guda, idan irin haka ta faru ha'kuri akeyi a barwa Allah ikonsa cikin kudirarsa sai kaga wata shekarar an samu madadi. Wannan yarinyar Allah Ya rubuta ba mai nisan kwana ba ce."
A ajiyar zuciya ya dan sauke a hankali ya furta." Hajja na yi hakuri tuntuni ai na barwa Allah wataran muma duk na hakane, amma har yanzu ina jin wani yanayi a tare da ni wallahi tunda aka haifi yarinyar nan Ubangiji Allah Ya dora mini tsananin sonta shiyasa nake jin rashinta kamar na babban mutum."

"To ai dama hakane duk dan da ba zai yi nisan kwana ba sai Allah Ya jarrabi iyaye da tsananin sonsa. Ka godewa Allah bisa ni'imomin da ya yi maka sai kaga ya sake yi maka wani tagomashin domin shi Ubangiji yakan jarrabi bawansa da abubuwa da yawa idan ya ga ya yi hakuri sai ya kawo masa d'auki."

Ya girgiza kansa a nutse ya furta." Allah Ya ba mu dangana.
Ya dubi inda nake zaune a hankali ya ce." Zan koma sama ki biyo ni da abinci."
A hankali na ce." To me zaka ci sai na shiga kicin na yi maka da kaina yanzu."
Ya juyo yana kallona kafin ya furta." Falalu bai yi ba ne."
''Ya yi."
Na fad'a ina dubansa sai ya ce." To ki kawo mini kawai ke ki huta."
Haka yake tun dama can bashi da matsawa akan lallai sai na yi masa abinci. Idan na yi masa zai ci da godiya da yabawa idan ma ban yi masa ba zai ce don me ba, zai ci na wanda ya saba wato Falalu. Wad'annan halayensa na saukakawa suna taka muhimmiyar rawa wurin ganin na bi shi ko da kuwa ya 'bata mini rai a wasu lukutan.
Na sameshi zaune saman sofa da laptop a gabansa amma hankalinsa baya kanta Yana duba wayarsa ne.
Na ajiye kayan abincin saman daddumar da yake zama idan zai ci abinci.
Ya kalleni yana fad'in." Zo ina so na yi magana dake."
Gabana ya dan buga kad'an saboda ina jin tsoron kada ya ce zai kwanta da ni jikina da d'aita ban dawo daidai ba, duk da jinin ya d'auke amma har yanzu ban ji ni yadda nake ada ba, kuma ban yi wani gyara ba, ba ni da nutsuwar yin hakan saboda rashin nutsuwa da rashin sukuni dake tartare da ni da mutanan gidan.
Na zauna a d'an tsorace Ina sake nazartarsa. Ya riko hannuna yana fad'in." Menene naga duk kin firgice ko kin san abinda zan gaya miki?"
Girgiza kaina na yi a hankali na ce." A a ban sa ni ba."
Ya nisa kafin ya ce." Kin san da cewa ni dake duka AS da AS ne, kin san ciwon da ya yi sanadiyar rasuwar baby Aish?"
Gabana na bugawa nake kallonsa na ce." Ya aka yi kasan hakan bayan ni ba a gwada ni ba."
Ya ce."likita ne ya yi mini bayani jininmu bai daidaita ba ga yanayin ciwon da aka haifi Nana dashi da karfinsa. Ni dama na san As ne, ke ce ban san naki group din ba.
Amma domin tabbatarwa zan kira likitarki ta zo har gida ta yi miki gwajin idan sakamako ya fito sai mu yanke shawara ko."
Shiru na yi bakina ya yi nauyi na kasa furta komai. Wace irin mummunar 'kaddara wannan, duk da Ina da yara a wani wajan amma ina so na haihu da mutumin nan. Hawaye masu zafi suka ciko Idona, babu abinda nake nazari da tunani sai illar ciwon nan da wahalhalunsa. Ko naki ko naso dole na samawa kaina lafiya na ciri kishi na kyale mutumin nan ya yi aure ya haihu.
Shawara ta gaba kuwa na ha'kura da haihuwar gabad'aya domin kuwa duk mu ukun ni dashi da abinda zamu haifa zamu kasance cikin wahala da zullumi.
Kamar ya san tunanin da nake yi kenan ya ce." Ke ni fa duk wasu canfe canfe da za a yi akan wannan lamari ba zan yarda ba. Da can ai auran ake yi babu abinda yake faruwa sai yanzu zasu zo su rikitawa mutane lissafi."

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na dube shi jikina duk a mace na ce." Ban gane abinda kake nufi ba."
Ya ce." Ina nufin ko an gwada ki an tabbatar da cewa ke din ma As ce za mu cigaba da haihuwarmu a haka, domin ba zan aminta da wannan yahudancin ba."

"Ba yahudanci ba ne Yallabai zamani ne ya zo da hakan, kuma ana samu sau'ki idan an bi ka'idoji, maganin ayi to kada a fara ni dai Ina ganin mu nemi mafita ta wata hanyar amma dai kada mu zo muna haihuwa yara suna mutuwa gashi kai baka da juriya."
Ya bata rai yana ce wa." Ba ni da juriya kamar yaya, magana za ki gaya mini."
Shiru na yi ban tanka masa ba ganin yadda ya sha kunu.
Ya cigaba da cewa.'' To ba za ma a gwadakin ba, na fasa na kuma k'adaita Allah d'aya ne duk abinda ya sami rayuwata daidai ne haihuwa kuma ni dake dole mu yi ta."

Na daure sosai don ba na so na fadi maganar da zata tunzura shi. Haka kawai tunda Baby ta rasu nake dan tausaya masa, saboda ganin yadda ya kidema ya kasa jurewa, amma zahirin gaskiya abu ne da zai yi mutukar wahala mu haihuwa muddin jinninmu ya zo daya to tabbas akwai kalubale mai yawan gaske...✍
Tofaa!!
MUJE ZUWA
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu.

Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*21*
Na daure sosai don ba na so na fadi maganar da zata tunzura shi. Haka kawai tunda yarinyar nan ta rasu nake tausaya masa wallahi. Na ce
"Nazari zaka yi ranka ya dad'e, kasan wani abun yakan shaf.......ban kàrasa ba ya katse ni a harzuke yana fad'in." Kin ga ki yi mini shiru Amina ya isa haka, na gane ki fa tuntuni ba kya son haihuwa tare da ni dama shiyasa rashin yarinyar ban bai wani dame ki ba dalili anan shine kina

da wasu yaran da wani namijin ni kadai ne nake kukan tashinta ke kuwa me ki ka fasa komai kina gudanarwa na abinda ya shafe ki, yanzu na gaya miki halin da ake ciki kina nema ki yi mini maganar banza akan wani banzan dalili."

Kawai sai na saki baki Ina kallonsa da d'umbun mamaki a tare da ni. Lallai da ana bud'e zuciya wani ya gani dana bude masa tawa ya ga yadda take cike da tausayinsa akan abinda ya shafemu bakid'aya.

Ya rufe idonsa sosai yana ta fad'a ta inda ya shiga ba tanan yake fita ba. Na yi shiru ban tanka masa ba, har sai da ya gama tukkuna na sassauta tare da fad'in." Ka yi hakuri idan maganata ta bata maka rai, amma ka yi mini gurguwar fahimta, ni ba haka nake nufi ba."
Ya janyo Lopton dinsa yana fad'in." Ki tashi ki je kawai ba na son dogon sharhi, na fahimci inda ki ka dosa zan nemawa kaina mafita."
Ban tashi ba sai ma sake matsawa da na yi kusa dashi na dafa hannunsa a hankali murya na rawa na ce.'' wallahi ina son Haihuwa da kai Allah Ya taimaka ban fadi maganar nan don na bata maka rai ba sai don nema mana mafita gabad'ayanmu, amma da zaka tona zuciyata zaka ganta cikin tsantsan damuwa da fargaba halin da muka tsinci kanmu a ciki."
"Ki tashi ki fita don Allah, ba na son wata magana, akwai abinda zan duba."
Na kalle shi naga ya yi mugun murtuke fuska irin wanda bai ta'ba yi ba mini ba, ban sake cewa komai ba na tashi jikina a sabule na sauka kasan da tunanin hanyar da zan bi wajan warware abinda yake shirin tunkaro mu.
Muna tsaka da wannan rikicin ni dashi Inna Uwani ta sauka a gidan. Sai lamarin ya kara lalacewa wanda har na fara hasashen gaskiyar maganar Hadiza akan inna Uwani tana jifan auranmu.
Dama a cikin jego nake dalilin da ya sanya kenan wata danganta ta aure bata ratsa tsakaninmu ba.
Da farko na yi zaton ya d'auke kansa ne ga lamarin duba da halin da nake ciki sai kuma na ga ashe ba haka ba ne, yau kwanana sittin da biyar da haihuwata zaman ya'ki dadi a junanmu. Yadda na so ni da shi ace mu kashe mu binne matsalarmu babu wanda ya ji ko ya gani amma abin ya fasskara domin duk yadda na so da mu zauna lafiya ya'ki fahimtar hakan. Har yanzu yana nan akan bakansa na cewa ina kyamatar hada jini da shi. Gabad'aya ma ya juyar da maganar ya dangatata da ni, ya mance abinda ya asassa faruwar mutuwar abinda muka haifa.
Wannan dalilin ya sanya na janye jikina dashi domin a duk lokacin dana hau samansa da b'acin rai nake saukowa ya canza mini gabad'aya kamar ba shine mutumin nan mai sau'kin hali da fahimta ba a wasu lukutan, yakan zame mini kamar wani mara wayo.
Ban daina gaishe shi ba, haka zalika kuma ban daina yi masa girki ba a duk lokacin da ya bukaci hakan amma kamar yadda ya nuna baya buk'atata a kusa dashi ni ma haka nake nunawa. Sai dai muna takatsantsan idan mun hadu a falo babu wanda zai fahimci muna da matsala da juna.

Maganarsa d'aurin auransa da Hauwa ta tashi gadan gadan. hakan bai daga mini hankali sosai ba domin tunda sakamakon jini ya fito a tsakanina dashi na cire son zuciya a raina ina jin zan iya bashi goyon baya dari bisa dari ya auri mata hud'u domin cikar muradinsa. Sai dai yanayin zamana a gidan shi yafi damuna domin kuwa soyayyarsa da ya dasa mini ita a kahon zuciyata tana nan bata gushe ba, ina kaunarsa har yanzu ina kuma kishin ganin wata mace a kusa dashi.
Abinda ya yi ta damuna kenan a cikin kwanakin nan wanda har na gaza jurewa na kira Anti Yagana a waya na sheda mata halin da ake ciki. Itama abin ya girgizata sosai, amma shawarar da ta ba ni shine kawai na yi hakuri na bi abinda yake so mu barwa Allah lamarinsa abinda tunda aka somi duniya akeyinsa wani nasara ba zai zo ya canza ba.
Na jima Ina nazarin maganganunmu da anti Yagana kafin na sauke ajiyar zuciya da ro'kon Allah Ya kawo mana dau'ki gabad'aya.
A ranar na shirya tunkararsa da amincewar bukatarsa
na shirya da daddare cikin kayan bacci masu kyau na yi barin turare a jikina. Sannan nasa hijabi mai tsayi na fita da zumar samunsa mu yi maslaha domin zamanmu a hakan yana damuna sosai.
Abin mamaki da ban tsoro sai na ga inna Uwani a wajan matattakalar benensa da wani koko a hannunta da gajeriyar tsintsiyar kwakwa tana ta yarfa abinda yake cikin kokon.
Kamar na koma da baya saboda fargaba da kuma tsoro sai kuma na yi shahada na tunkari wajan Ina hirji da manyan addu'oi da zasu yi mini kariya.
Ganina ya tsoratata ainun. A dabarbarce ta fara ko'karin magana tana ce wa." Maganin baki da mugwayene na ke yayyafa muku a gidan Amina domin naga alama ke da mijin naki bakwa neman tsari."
A nutse na ce." Muna neman tsari daga miyagun mutane aljanu da mayu, kullum cikin addu'a muke kuma in sha Allahu rabbi babu wani abu da zai same mu inna Uwani."
Jiki a mace ta furta." Duk da haka dai, ai ku mutanan yau ba ku san abinda yake faruwa ba." Ban ce mata komai ba na nufi matattakalar benan ina addu'a na fara hawa a nutse ban sanya a raina cewa abinda ta yi zai yi tasiri a kaina ba.

Bangaran Inna Uwani kuwa jiki a sabule ta shige masaukinta domin kuwa aiki ya b'aci tunda sharad'in da malamin ya bata cewa sai dare ya tsala tukkuna zata gabatar da aikin yayin da sahu ya d'auke ba a buk'atar a ga gilmawar wani bil'adama lokacin da take gudanar da aikin akwai aljanin da yake taimaka mata. Fitowar Amina kuwa ya dakusar da tabbatuwar aikin da ta so ta gudanar domin raba tsakanin ma'auratan.

Na same shi yana ta aiki a computer, aikin kenan dama a wasu lukutan bashi da hutu ko kad'an, yau yana can gobe yana nan idan an dawo gida ayi ya lissafi abinda ya shiga da wanda ya fita.
Ya dago kansa ya kalleni a lokacin da nake ko'karin karasawa kusa dashi.

Bai ce mini komai ba ya mayar da kansa domin cigaba da abinda yake yi na zauna a hannun kujerar da yake kai na dora hannuna a kafadarsa Ina dan shafa saman kansa a hankali a hankali.
Na san yana masifar son kamshin kalolin turarankan da nake amfani dashi dalilin da ya sanya kenan na sanya sosai a kowane kusurwa ta jikina.
Bai tanka mini ba, yana ta aikinsa, abin ya fara ba ni mamaki domin na fi kowa sanin halinsa akaina ban kusanceshi ba ma yana susucewa ina ga na kusanceshi Kuma. Ga ni yanzu ina yi masa abubuwa na jan hankali amma ko gezau bai yi ba.
A hankali na sanya hannuna na dago ha'barsa muka kalli juna. Na marairaice fuska kamar mai shirin fashewa da kuka na ce." Wallahi abinda ka tsira bai yi maka kyau."
Ya yi kokarin janye fuskarsa na sake juyo dashi cikin ko'karin sace zuciya na ce." Ka kalli tsabar idona ka gani cike take da sonka da begenka uwa uba kuma da sha'awarka me zai sanya ka dinga fushi da mai k'aunarka me na yi maka mai tsanani haka my Habibi kada makiya suyi mana dariya fa."

Ajiyar zuciya ya sauke ya janye fuskarsa yana ko'karin rufe computer na zira hannuna cikin rigarsa ta bacci wadda botiran sama suka cire a nutse na fara shafa kirjinsa da yake cike da lallausan gashi sai ya fara sauke ajiyar zuciya yana cire hannuna ina mayarwa har dai muka fara kokawa, ya rike hannuwana duka biyun ganin hakan yasa na rikota kansa gabad'aya na kanainayeshi."
Rintse idonsa ya yi ya fara sakin nishi. Ya ki ya rike ni, sai ni ce nake ta makaleshi a jikina. Ya ki'dime sosai sakamakon kamo bakinsa da nake ko'karin yi. Ido a shagide ya ce ." Ya kike so na yi miki, kin ce ke ba za ki haihu da ni ba, to me zai sanya ni kuma na cigaba da wahalar da kaina wajan fitar da 'kwayoyin haihuwata a banza suna bin rariya ba zan iya ba gaskiya."
Na sa'kalo wuyansa muna kallon juna na furta." Na amince my love dama kaine fa baka fahimce ni ba, amma idan an yi duba na tsanaki za a gane maganata a kan hanya take amma tunda haka kake so na amince da ra'ayinka. Ubangiji Allah Ya ba mu masu albarka."
Ya tsira mini ido yana kallo domin so ya tabbatar da abinda yake zuciyata. Na ce." Wallahi na amince har cikin zuciyata.
Sai ya sauke ajiyar zuciya ya dan saki fuskarsa. Kafin ya fara yun'kurin tashi dani a jikinsa na rike wuyansa yayin dashi kuma ya tallafe k'uguna wanda kafafuna suke ma'kale da nasa k'ugun. Haka muka nufi gado ina ta raramo bakinsa ina sawa anawa.
A daran ni dashi ban san wanda ya fi gwadawa wani soyayya ba. Mun ji dadin junanmu sosai mun gamsu da juna fiye da kowane lokaci.

Washe gari da safe kenan kafin na sauka kasa yake gaya mini maganar d'aurin auransa da Hauwa a farkon watan musuluncin da za mu shiga don har manya sun gama komai ya tura mata komai na hakkinta. budurwa ce amma mai shekaru don yadda yake gaya mini ta haura talatin da biyar hakan ya tabbatar mini da cewa ta dan girme mini. Ya nuna mini hotonta

dake wayarsa tana sanye da kayan likitoci domin ma'aikaciyar asibiti ce. Sannu a hankali ba tare dana tambayeshi ba yake ya gaya mini yadda suka yi da ita.
Wai tana son a yi shagulgula irinsu dinner da dai sauransu shi kuma ya ce baya so kawai a d'aura aure ta tare.
Ni dai murmushi kawai nake yi ban tofa tawa ba domin wani abu ne yake ta tsunkulina a can kasan zuciyata wanda na san ba komai ba ne face kishi.
Inda Allah ya taimake ni ma na fita diri da zubin jiki mai kyau tunda ni ko'ina na jikina a cike yake dam. Ita kuwa bata da kirji k'ananu ne sannan bata da baya a tsaye take sai dai akwai kyawun fuska kwarai da gaske kuma doguwa ce don tafi ni tsayi sosai amma kuma  akwai wayewa irin ta 'yan boko. wannan kuma ni ma ina da nawa ilimin daidai gwargwado.
Da ya ce mini ya bata miliyan goma kudin kayan lefe da kwalliya ban damu ba dalili ni na san na samu fiye da abinda ya bata a lokacin d'aurin auranmu a yanzu da jarina da nake juyawa da irin alheran dana samu ta 'bangaransa sun tasarwa miliyan arba'in, alhamdulillahi babu abinda zan ce da Ubangiji.
Ganin ban ce komai ba sai ya dube ni cikin lallami ya sake cewa." Kema na baki kudin kitso da lallenko?"
Na kalleshi da murmushin dana kakalo babu nishadi na ce." E ni ma ai zan gyara kafin amaryar ta zo, ko da yake ai ba zan kamo kafarta ba a wajanka."
Ya riko hannuna yana fad'in."  Duk abinda zan gaya miki ai ba zaki yarda ba amma kina can cikin zuciyata rayuwata ba zata inganta ba sai dake."
Dariya maganarsa ta ba ni. Na ce." Lallai kam to na gode, yanzu me kake so ka ci domin na shiga kicin na yi maka."
"Kunun tsamiya da kosai."
Na ce." An gama ranka ya dad'e."
Na tashi da sauri Ina cewa." Nan da minti talatin zan kawo maka."
Ya bi ni da kallo a yayin da nake ko'karin fita daga d'akin yana cewa." Allah Ya yi miki albarka."

Ina sauka kasa na samu Hajja da inna Uwani a zaune suna magana. Sakkowata ta d'auki hankalinsu gabad'aya. Inna Uwani ta sunkuyar da kanta yadda na lura bata son had'a Ido dani. Cikin zuciyata na ce ni bana daya daga cikin mutanan dake fallasa asirin mutum. Idan halinkine wataran masu gidan zasu ganki, kuma in sha Allahu babu abinda zai same ni.
Na gaishesu gabad'aya suka amsa Hajja sai murmushi take don ta ji dadin ganina na fito daga wajan maigidan.
Domin na kara mata nishadi na ce." Zan shiga kicin shiryawa maigidan abin kari."
Ta ce." To shikkenan Allah ya yi niki albarka Amina.
Sosai nake jin dadin Addu'ar da take yi wannan yana daya daga cikin dalilan da suka sanya nake ji a zuciyata duk rintsi duk wahala zan zauna tare dasu a gidan.
Bayan na kammala komai na kai masa sai na sake saukowa domin naje na yi wanka....✍
*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k  akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*22*
Dama tare muke da Hadiza a d'aki daya ina shiga d'akin na sameta tare da Yusi suna hira da yake yau asabar babu makaranta sai wajan sha daya tukkuna yake tafiya islamiyya sai yamma kuma ya dawo.
muka gaisa gabad'aya a gurguje na shiga toilet domin watsa ruwa. Ina ciki na dinga jin magana kasa-kasa Hadiza ce take waya kuma na ji tana ambatar sunana. Ban kawo komai a raina ba domin dan zaman da na yi da ita na fahimci cewa dole akwai k'auna irin ta 'yan uwantaka a tsakaninmu ba zata cutar da ni ba. Ina fitowa take cewa da ni." Fati ce babu lafiya, tana kwance a asibitin Malam Aminu an yi gwaji sakamakon ya fito tana d'auke da cancer mama. Hankali ya tashi ainun domin kuwa nasan ciwon yana da illah.
Cikin damuwa na ce." To yanzu ya ake ciki ya jikin nata."
Cike da alhini don har sai da hawaye suka zubo a kumatunta ta ce." Kin san mijin nata ba wani kudi ne dashi ba akwai dai rufin asiri kuma tunda suka tara yara nauyi ya yi masa yawa da kyar ma yanzu suke samun ci abinci yanzu yaranta biyar.
To shine yake gayawa Babanmu shi ya gaji ba zai iya cacar asibitin Malam ba domin bashi da iko a dawo da ita gida ayi mata na hausa kawai. Shine Ummanmu take gaya mini yanzu." Tasa hannu goge hawayen da yake ta zarya a kumatunta.

Na ce." Ba za a yi haka ba Hadiza ni menene amfanin arzikin nawa ai saboda irin haka nake nema ba dare ba rana in sha Allahu babu abinda zai gagara, ki kira mini Ummantaku a waya yanzu sai mu yi magana."
Da sauri ta d'auki wayarta dake ajiye ta kirata.
Na kar'ba muka gaisa na ce." Ashe Fati ce bata da lafiya Umma amma me yasa ba a gaya mana da wuri ba."
Da damuwa a tare da ita tace." Yanzu ne tura ta kai bango shiyasa na ce Hadiza ta taho gida domin ta taya ni jinyarta ga yaranta a gabana uban yana nuna gazawarsa nema ma yake ya sakar mana dawainiya."
Na ce." Yanzu nawa ake bukata a asibitin wajan yi mata aikin."

Ta ce." Ai kin san jan kudi irin na asibitin Malam wai suna buk'atar miliyan shida domin yi mata aikin saboda kada d'ayan ma ya harbu.''
Na ce." To ku kwantar da hankalinku in sha Allahu rabbi zan sanya Hamusu ya je asibitin ya biya kudi.....Kafin na kàrasa ta ce." Ki dai sanya shi ya tura a acct din ita Fati din kin san mijin nata da zargi kada ya juyawa mutane magana idan ya zo sai na yi masa bayani kece ki ka biya kudin aikin, zan yi wa babanku bayani ma."
Na ce." To shikkenan zan kar'bi acct din a wajan Hadiza Ubangiji Allah Ya bata lafiya."
Ta amsa da "Amin Ya Allah, mun gode sosai Amina Allah Ya yi miki albarka."
Na ce." Babu godiya a tsakaninmu Umma Fati kanwatace don na yi mata abu ba komai ba ne.
Mukayi sallama na kashe wayar na mik'a mata wanda har zuwa lokacin kuka take kashir'ban tana share hawaye kamar wadda aka ce mata Fati din ta mutu.

Na ce." Hadiza ki yi shiru don Allah, a yanzu Fati babu abinda take buk'ata sai addua. Kuma in sha Allah idan kudi suna magani, na yi alkawarin zan yi daidai gwargwadona sai kuma mu bi ta da addu'ar samun lafiya daga wurin Allah domin shine yake saukar da cuta, ya kuma bada sau'ki."
Ta goge hawayen fuskarta tana sake yi mini godiya. Ban ce komai ba na nufi wardrobe dina domin sanya kayana a jikina.

Da tunanin rashin lafiyar Fati na yini a cikin raina. Gashi na yi ta kiran wayar Hamusu domin mu san yadda za a yi bata shiga ban san menene dalili ba. Amma na bari da daddare sai na kara trying na ji, Hamusu baya kashe wayarsa a duk lokacin da aka kira shi ana samunsa.
Daddare ina d'akin maigidan Hamusu ya kira, ban yi mamaki ba domin lokacin dana kira shi ban same shi ba sai na kawai tura masa text wanda na san koda matsalar network ne idan ya saki zai gani.
Lokacin maigidan yana bandaki don shima bai jima da shigowa ba, kuma baya zaman cin abinci sai ya yi wanka tukkuna.
Na daga wayar da zuciya daya Ina fad'in. " Hamusu lafiya ake ta kiran wayarka bata shiga."
Ya ce." Wallahi anti Amina yini akayi ana ruwa anan duk network din layina ya sauka sai yanzu ya dawo.
Na ce." Ni ma na zargi hakan shiyasa na ce bari na yi maka text na san zaka ga ni.
Daidai lokacin da yake ba ni amsa shi kuma ya fito daga band'akin... Na ce." Wallahi kuwa d'azu muka yi waya da Ummansu cewa jikin nata ya yi tsanani, asibiti sun bukaci kudi zan dai yi maka magana ta Whasap idan an jima sai muga yadda za a yi."
Ya ce." To shikkenan anti ina sauraranki.''
Na kashe wayar tare da ajiyeta a gefena na dube shi yana zaune kan sofa yana dan mutsika cream a jikinsa. Amma canzawarsa ta ba ni mamaki fuskarsa babu annuri bai kuma kalle ni ba ya ce." Wanene ma Hamusu ne?"

Ya fad'a babu annashuwa a tare dashi. Kallonsa nake da mamakin tambayarsa ai na d'auka a iya dad'ewarmu dashi ya fahimci wanene Hamusu tunda har tafiya mun had'a shi a lokacin da muka je duba Kamalu a makaranta wanda har alherin kudi ya yi masa, amma yanzu saboda tada zaune tsaye yana tuhumata.
Shiru na yi ban iya ce masa komai ba.
Ya sake cewa." Wanene Hamusu Amina?"
A nutse na ce." Kanina ne shi, abokin kasuwancina kuma mahaifinsu Yusi ne tunda kanin Ubansu ne."
Ya zuba mini ido da ce wa." Ni ban haifesu ba kenan shiyasa kike so ki nuna mini iyakata."
Na ce." Ba haka nake nufi ba."
"Okey wace magana na ji kuna yi fitowata daga bandaki ki ka katse har kina cewa zaku hadu ta whasap."
Cikin ko'karin kama mutuncina na ce." Ba wata magana ba ce ranka ya dad'e wani abu ne da shafe ni."

Ransa ya sake 'baci." Okey shi Hamsun ne yake auranki da har ni ban isa ki gaya mini abinda ya shafe ki ba sai shi, ni namijin hotiho ne ko, sai a shimfida nake namiji amma a zamantakewa ba ni da amfani ko."
Na ce." Wai don Allah me yasa kake nema ka canza mini magana ne nifa ba hak...
Ya buga hannun kujerar da yake zauna yana kallona da kishi da b'acin rai ." Ke ba ki ji kunyar yin magana da wani namiji a d'akina ba Amina, wai me yasa kike nema ki raina mini hankali ki mayar da ni shashasha, ni zaki ciwa fuska a gidana, a kuma d'akina ki dinga waya da wani dan iska, har kina kashe waya saboda kada na ji abinda zaku tattauna, ba ki d'auke ni mutum ba ko."
Cike da mamakin fusatarsa na ce." To da kuma ka ce baka gane shi ba, Hamusu ne fa ba wani ba, a tunanina ko zaka zargeni da wani namajin ba zaka zargeni dashi ba tunda kanin uban yarana ne, kuma kasan dole a kowane lokaci alaka ta had'a ni dashi dalilin Kamalu da Yus..... "Me yasa baki aure shi ba." Ya katse maganata yana huci ya cigaba da ce wa." Idan zargi zan yi akanki shine mutum na farko da zan zarga domin alak'ar(ALAKAR ZUCCI) Littafin marubuciya (Maidamu) kada ku bari a baku labarinsa. domin alak'ar da take tsakaninki dashi ta yi muni, wane irin cin fuska ne wannan."
Shiru na yi ban ce masa komai ba, amma raina ya gama baci da irin abinda yake yi mini, wani lokacin yana kasancewa mai sanyi da sau'kakawa a cikin al'amuransa, amma a wasu lukutan idan yana masifa har mamaki yake ba ni, sai ya rufe idonsa kamar bashi da ilimin Arabi da boko."

"Ba za ki gaya mini akan abinda kuke magana ba ko?" Ya fad'a yana tsatstsare ni da Idonsa. A nutse na ce." Fati ce bata da lafiya shine aka bukaci kudi a asibiti za a yi mata aiki, to dama akwai kudina a hannunsa shine na ce ya cire ya tura musu."
Ba tare da ya kalleni ba ya ce." Wacece Fati?"

" 'Kanwata ce, itace take bin Hadiza a dakinsu."

"Shine ba za ki sanar da ni ba saboda kina so duniya ta zage ni ko?kin san dalilin da ya sanya suka kira ki a waya suka gaya miki domin sun san kina aurena akwai hanyar da zasu samu mafita, sai ki ka za'bi kiran kanin tsohon mijinki, kina gaya masa ya basu kudin maganin ko?"
Kaina na dafe da yake sarawa. Na dago na kalleshi Ina auna maganganunsa da basu da tushe balle makama. Na tsira masa Ido ina ayyanawa a raina cewa babu mamaki rikicin tsufa ne ya fara kama shi amma idan ba haka ba ya za a yi ya nemi ya canza mini manufa bayan ba haka ba ne a cikin zuciyata.
Ya ce." Kin yi shiru saboda kema kin san ba ki da gaskiya ko?"
Na dai yi shurun ban tanka masa ba, saboda ba mu jima da sasantawa ba, ba na so akan wannan 'karamin dalilin da yake nema ya mayar dashi babba mu koma 'yar gidan jiya.

"Ba za ki ba ni ha'kuri ba kenan?"
Cikin dariyar da ban san lokacin da ta sub'ce mini ba na ce." Ka yi hakuri Baba, ba zan sake ba."
Ya girgiza kansa tare da mikawa ya nufi wardrobe dinsa yana cewa." Saboda kina waya da Hamusu ko kayana baki d'auko mini ba na gode miki Amina."
Wallahi shaf na manta domin hankalina ya tafi wajan ganin na samu Hamsun a waya an gama komai.
Daidai lokacin dana isa wajan da yake tsaye ya d'auko k'ananun kaya t-shart da short nicker na kar'ba daga hannunsa tare da cewa." To mu je na shiryaka."
Ya kuwa biyo ni zalo zalo! muka zauna a gefan gado yana ta kallon fuskata yayin da ni kuma na take ta danne dariyar da take yun'kuro mini.
 Bayan na taimaka masa ya shirya sai ya dube ni babu wasa a fuskarsa. Ya ce.'' Ki goge lambar Hamusu daga wayarki."
Da mamaki na ce." Me yasa Baba?"
"Ki goge dai kawai akwai dalilaina."
Ganin da gaske yake yi ya sanya ni ma na shiga nutsuwata sosai na ce." Kai ma kasan hakan zai yi wuya, mu yi maganata gaskiya da gaskiya my love, ba na neman fitina domin ba za ta yi mana dad'i ba, Hamusu ba kowa ba ne a wurina face d'an'uwana abokin kasuwancina, sannan kuma kafi kowa sanin dangatakar da take tsakaninsu da mijina na fari uwa daya uba daya suke, bayan wannan ba ni da wata alaka dashi, Ina ganin baka da hujja mai karfi da zaka ce lallai sai na goge lambarsa daga wayata.

Ya zuba mini ido da tsananin b'acin rai yake ce wa." Ba ni da hujja mai karfi ko?"
Juyar da kaina na yi daga barin kallonsa domin na lura maganata ta yi masa zafi.
Ya d'auki wayata dake ajiya a gefena, na bishi da kallo amma ban yi yun'kurin kwacewa ba, ina kallo ya goge lambar Hamusun daga wayar ya

dube ni." Ban yafe miki ba idan ki ka sake magana dashi, na san goge lambar ba zai dame ki ba tunda zai kira ki wataran saboda yana da taki. Idan ki ka ci amanata Allah Ya yi mini sakayya.
Hawayen da nake dannewa suka zubo. Na ce." To sai ka gaya mini zargina kake yi ko me? Ka san ko zan yi neman maza ba zan yi da Hamusu ba, domin kuwa kafi kowa sanin halina.
"Ni ba na zarginki, kawai na datse alakarku ne domin mutuncina da kike ko'karin ki zubar mini."
Na gyada kaina ban sake ce masa komai ba na tashi na bar masa d'akin.
Da takaicin abin na kwana a cikin raina, amma hakan bai hana ni zuwa na gaishe shi ba yana zaune wajan da yake hutuwa, muka gaisa babu sukuni bai dube ni ba ya ce." Ki dama mini kunun tsamiya dashi nake sha'awar karyawa."
Ban ce komai ba na tashi na fita. Minti talatin na gama tsaf na kai masa na ajiye tire din zan fita ya ce." Sannu." Kanzil ban ce ba na fita. Kicin din dai na koma na d'auko wanda na hadawa Hajja na kai mata har dakinta tunda lokacin bata fito ba. Kafin na shiga na ji maganarsu ita da 'yar'uwarta inna Uwani suna tattaunawa akan abinda ya shafi hidimar da take gabatosu. Muka gaisa ko da wasa ban nuna cewa na ji abinda suke cewa ba, kuma na yi kokarin ganin na boye bacin raina.
Na fita na nufi d'akina. Hadiza tana ta had'a kayanta a cikin kwataki na ce." Hadiza wai tafiyar ce ba zaki bari sai wani satin ba."
Ta ce." Zan dawo ai Amina, gabad'aya hankalina ne ya yi gida ina so naje naga jikin Fatin.'
Na ce.'' Ni ma in sha Allahu bada jimawa ba zan zo, Ubangiji Allah Ya bata lafiya"
Ta amsa da Amin." Kayan jikina na cire ina shirin shiga wanka ya shigo d'akin.
Lamari mai girma ne yake kawo shi d'akina dalilin da ya sanya ma kenan dana ganshi gabana ya fad'i.
Hadiza da sauri ta risina tana gaishe shi. Ya amsa fuskarsa a sake Yana dubanta da kulawa ya ce. " Ashe Fati ce bata da lafiya."
Ta ce. Eh wallahi yanzu ma shirin tafiya nake yi domin zuwa dubanta."
Sai ya kalleni yana cewa." Zata tafi amma ba ki gaya mini ba."
Shiru na yi. Ya kawar da kansa yana cewa da ita." Nawa ne abinda aka buk'ata?"
Cikin inda-inda ta ce." Miliyan shida ne?"
Ya ce." Me yasa ke ba ki same ni kin gaya mini ba, tunda ita ban isa ta ta sanar da ni ba."
Ta yi shiru tana dan murmushi ya ce." Ba ni lambar asusun da za a sanya kudin sannan zan sanya a kai ki gida don ba zan yarda ki bi motar haya ba."
Cikin sauri ta gaya masa lambar acct din Fati mai suna Salisu Fatima Fedlity bank.
Ya ce." Zan saka in sha Allahu idan kin je gidan ki gaishe mana dasu kafin mu zo."

Ta amsa da sauri tana cewa." In sha Allahu kowa zai ji, Ubangiji Allah Ya saka da alheri ya kara arziki mai amfani ."
Bai amsa ba ya fita daka d'akin.
Ta dube ni tana cewa." Amina don Allah ki kara yi mana godiya, ke kam Allah ya kashe ya baki, shi so yake yi ma ki fad'a masa hidimar 'yan uwanki ya yi miki."
Na dubeta babu yabo babu fallasa na ce." Hadiza ba wannan ba, ki nutsu dan Allah kada don kin ga ya ce haka ki nemi zubar mana da mutunci don girman Allah duk abinda kuke buk'ata ku gaya mini ba zai gagareni ba, amma ba na so ku tambayeshi yin hakan sai ya rage mini kwarjini da martaba a idonsa."
Ta ce." Eh kuma hakane to zan kiyaye in sha Allahu."
Na tashi na shiga toilet din da tunaninka masu yawa a kwanyata.

Hadiza kuwa kwafa ta yi cikin zuciyata tana ce wa'' Mutuncin banza da wofi ya dad'e b ai zube ba, saboda b'akinciki mutum yana so ya yi alheri kina dakusar dashi, sai mun tambaye shi din ki yi duk abinda za ki yi....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin

nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*23*
Bayan tafiyar Hadiza da kwanaki uku sai na ce bari na kira na ji ya taje gida domin na yi mamaki sosai da bata kira ni ba wai bahaushe ya ce 'Idan ka ji shiru lafiya ce.'
Babanmu na fara kira domin mun kwana biyu ba mu gaisa ba. Bayan mun gaisa sosai na tambayashi gida ya ba ni amsa da komai lafiya sai na ji bai sako mini maganar rashin lafiyar Fati ba. Lokaci kan'kani na fara nazarin wani abu a zuciyata.
Na ce." Baba ya jikin Fatin ina fatan  an yi mata aikin domin tun bayan barin Hadiza daga nan nake ta dakon kiran waya domin a sanar da ni halin da take ciki, wallahi hankalina ya tashi sosai da wannan ciwon da ya same ta.
Ya ce." Ai ta ji sauki tuntuni jiya ma ta koma gidanta, maganar aiki kuma ni ban san dashi ba, domin bayanin da mijinta ya yi mini cewa zazzabin typhoid da maleria ne yake damunta. Shine ya kawo ta gida domin a kwance take

sosai a can din, k'arin ruwa kawai nasan anyi mata da allurai shikkenan kuma kwana biyu kacal ta warware mijinta ya zo ya d'auketa da yaran suka tafi.
Cike da mamaki da mutuwar jiki na ce." To ikon Allah, amma ni ba haka Hadiza da Ummansu suka gaya mini ba, amma shikkenan babu komai Ubangiji Allah Ya bata lafiya."
Ya amsa da Amin kafin ya d'ora da cewa." Amina me yasa idan kin tashi yin alheri ne ba kya had'awa da Sakina tunda Hadiza ta dawo suke husuma a gidan sun hana ni shan ruwa Hadiza da uwarta sun had'ewa Sakina kai, kuma duk irin alheran da ki ka bata sun hana Umman Saminu, shin ko kema Murja ta lalataki ne."
Da sauri na ce." Wallahi a a Baba, sharrin ba na kowa ba ne face na Hadiza domin kuwa ni duk abinda na bayar gabad'aya gidan na basu ban ware kowa ba, ai kaga ko da salla d'inki iri daya nake yi musu."
Ya sauke ajiyar zuciya yana cewa." Ni ma na zargi Hadiza da d'aga mini hankali, domin kuwa tunda ta kaso auranta ta dawo gida ta zauna shikkenan gidan ya zama kamar sansani, itace fad'a da wannan itace fad'a da wannan."

Na ce." Baba ka yi hakuri kayi mata addu'a Allah ya fito mata da mijin aure, amma ya zama dole na kira ta a waya domin na ji dalilinta na yin hakan."
Ya ce." To shikkenan hakan ya yi Allah ya yi mini albarka."
"Amin Baba zan sanya Hamusu ya tura maka kudi koda da akwai buk'atar da zakayi."
"Na gode sosai Allah ya sanyawa dukiyarki albarka, ya kuma shirya miki zuriarki."

Muna yin sallama na kira Anti Yagana raina a b'ace na shiga sanar da ita abinda Hadiza da Ummansu suka aikata. Yanzu na gane karyar ciwo suka shirya da Fati domin su samu kudi a hannunà ban ta'ba kawo hakan a cikin raina ba domin zaman watannin da ta yi a gidana  ban ta'ba zargin zata cutar da ni ba, don  Ina ganin yadda take shiga damuwa a duk lokacin data gan ni, a cikin matsala.
Anti Yagana itama ranta ya 'baci sosai, ta dinga fad'a tana cewa dama tun farko sai da ta zargi hakan shiyasa a lokacin da ta tubure sai ta zauna mini ranta bai so ba, babbar damuwarta ma kofar da maigidan ya basu tunda da bakinsa yake cewa idan suna buk'atar wani abu su sanar dashi, wannan zai basu k'warin guiwar zubar mini da dan ragowar mutumcin da nake dashi a wajensa.  Ta ce lallai zata kira Hadizan ta ja mata kunne akan abinda suka shirya ba daidai ba ne.

Ni ma a take a lokacin bayan na yi sallama da ita na lalubi lambar Hadizan na kira minti daya ta daga da fara'ata muka gaisa a takaice na ce." Ba na neman wani 'karin bayani daga wajanki Hadiza na gode bisa abinda kuka yi mini, Babanmu ya gaya mini komai, yanzu Hadiza idan kudi kike so a wurina har sai kun shirya karya, me yasa ba zaki tambayeni ba."
Shiru ta yi ba tace komai ba. Na cigaba da cewa." Sannan duk uban kayan nan dana hada da na ci, dana sha, dana sanyawa babu abinda kuka bawa

Ummansu Saminu alhalin cewa na yi a rarraba har gidajensu Baba Sule shine kuka had'a gabad'aya babu wanda kuka bawa."
Ba ta ce mini komai ba ta dai yi shiru tana jina. Na ce."Wannan zama na farko ya kuma zama na karshe wallahi tallahi kada ki sake yi mini haka domin ni na tsani na zauna da mutum da zuciya daya amma shi da zuciya dubu yake zaune da ni, kina a matsayin 'yar uwata kina cin dunduniyata ban ji dadin abinda ki ka yi ba wallahi."

"Kin ga Amina ya isa haka don Allah ba za ki kira ni a waya ki nemi gaya mini magana ba, shi ma Babanmu bai san kan ciwon ba shiyasa ya ce miki zazzabi ne, kudi kuma ai ba ke kika bayar ba balle ki ce wani abu, arzikinan fa kema takarsa ki ka yi baki gada ba, don haka baki da bakin yi wa wani gori."
Tsaki na ja na kashe wayata domin idan za mu kwana a haka ba zata damu ba tunda dama mun saba cacar baki tun muna yara. Kuma tun a wancan lokacin take nuna b'akinciki da kishi dangane da dukkanin alherin da zai tunkaro ni.

Bayan kwana uku na samu Hajja domin Ina so na yi magana da Hamusu kuma ina tuna Allah ya isar da ya yi mini. Ban ta'ba kai k'ararsa wurin mahaifiyarsa ba, ba don baya yi mini lefi ba, kawai ina dannewa ne domin zuwa yanzu na saba da kyawawan halayensa da munana. Ban ga dalilin da zai sanya ni a matsi ba bayan shi koyaushe cikin walwala yake wanzuwa mussaman da hidimar auransa take matsowa.

Duk na gaya mata yadda mukayi dashi da Allah ya isan da ya yi mini idan na yi magana da Hamusu. Ta ce." Ki yi hakuri zan yi masa magana, ai kina da gaskiya to me zai sanya a tauyeki bayan abokin kasuwancinki ne, ai ba wata hurd'ar banza kuke yi balle ya nuna kishinsa, ki kyaleshi kada ki sake yi masa maganar ki bar komai a hannuna yau din nan zan yi masa magana."
Na yi mata godiya sosai na tashi jikina da k'wari da karsashi domin na san dole idan ta yi masa magana ya janye abinda ya taka.
A daran ta yi masa maganar kuwa dalilin da ya sa na fahimci hakan canzawarsa domin maganar duniya babu kalar wadda ban yi masa ba ya share ni. Har tu'be kayana na yi a gabansa na tsaya zurr da ni haihuwar uwata bai kalleni balle ya nuna sha'awarsa. Bakam kawai ya yi mini na gama neman maganata na ha'kura domin ganin ban samu dan tayi ba.

Ban d'auki lamarin da zafi ba shiyasa har yanzu na kasa gano dalilin fusatarsa domin ni sai nake ganin wannan lamarin kadai ba zai sanya shi yin wannan gagarimin fushin ba.
Wasa wasa abin yana ta nisa, domin ni na yi zato duk rintsi fushi da gabar da yake da ni ba zai wuce kwana biyu sai gashi yau kwana takawas kenan ba ma ga maciji.
Hankalina ya fara tashi domin gaskiya ban fiye son gaba ba a rayuwata shima kuma na lura ba dabi'arsa ba ce domin da ya fara ma yake watsarwa

ya neme ni da shiri, wannan karon kuma ta yi tsanani, ba amsa gaisuwa ba kuma hira balle a kai ga maganar kwanciyar aure.
Na bi duk hanyoyin maslaha domin ganin ya sauke fushinsa amma ya'ki don da ya lura ma abin ya dame ni sai ya kara zage dantse ya yi ta cin magani ya'ki kallona. Ni kuwa a raina nace na san yadda zan yi maka.
Da daddare misalin sha daya da wani abu na hau saman nasa.
Kallo na same shi yana yi a katuwar tv din dake kafe a bedroom din nasa. Na yi mamaki sosai domin kallo bai dame shi ba. Cikin zuciyata na ce rai dangin goro kenan, yau babu lissafi da latsa computer.
Kai tsaye tibin na nufa na kashe na juyo muka had'a ido yana dan hararata amma bai ce mini komai ba.
Na yi murmushi tare da girgiza kaina, hijab din da yake jikina na cire na cillar dashi a gefe na yi tsaye a jikin tibin. A lokacin dana sanya kayan ni kaina sai da kunya ta kama ni, amma nasan wajan wanda zan ni idan ya gan ni dasu lada zan samu.
Kaya ne irin na 'yan iskan turawa wanda basu da maraba da tsirara wandon irin mai igiyar nan ne a gefe da gefe duk ya shige mini tsakani. Rigar kuwa dan mitsitsin soso ne da ya dan rufe saman kirjina amma da ita ma gwara babu tunda duk gasunan sun tullutso waje.
Ina ganinsa da saurin gaske ya d'auke kansa daga barin kallona. Ni kuwa na taho da sassarfa ina rangaji na nufe shi ban tsaya komai ba na fad'a jikinsa na tallefe kansa a kirjina matse shi nayi sosai ina nishi da yin wani irin abu da bakina wanda ba na yin hakan sai muna biyawa juna bukata.
Ya ki'dime ainun! ya fara ko'karin cire ni daga jikinsa yana dan dukan mazaunaina.
Cikin fitar hayyaci murya a sarke na ce." Gaskiya ba zan jure ba, ina cikin bukatarka don haka ka yi mini kawai sai ka cigaba da yin gabar tunda baka jin rarrashi."
Na zira yatsana karami a kunnensa ina yi kamar ina sosa masa.
Da wani irin sauti ya furta." Ni kuma ba ni da wani karsashin da zan yi don ba ni da lafiya ma."
Hannuna yana yawo a sassan jikinsa cikin shgawaba na ce." Ashe kuwa zamu kwana a haka don wallahi ni mai raba ni da kai a yanzu sai Allah."
Sautin murmushinsa na ji ya ce." To shikkenan mu kwana a hakan ni ba zan damu ba."
Na dube shi naga yana lumshe Ido na fahimci baya so ya bud'e  naga halin da yake ciki.
A hankali na dan sauka daga jikinsa sai yayi sauri ya bude idon yana kallona da idanunsa da ya fara canzawa.
Kafafunsa naja suka mike sosai yana ta kallona bai ce mini komai ba na zare jallabiyar da take jikinsa na jefar. Komai na jikina na cire sai ya janye idonsa daga gare ni yana sake lumshe idonsa.
Jin ina ko'karin cire gajeran wandon dake jikinsa da sauri ya bud'e idonsa yana fad'in." Ke menene haka?"
Na 'kankance Ido ina fad'in hakkina zan kar'ba."

Dariya ya sa yana jan tsaki ya janye kafarsa yana ko'karin mayar da wandon na ri'ke da kyau.
"Ai ka ce sai dai mu kwana ko? Ni idan zan kwana ma ban damu ba domin yadda nake jin kaina yau na fi zakanya kuzari."
Ya yi mini shiru bai tanka mini ba.
Ko'karin hawa gadon yake yi na bi shi na danne ya yi flat ni kuma ina samansa cikin gaggawa na fara raromo bakinsa. Duk ciccijiewar da ya dinga yi sai da dauriyarsa ta 'kare ya rasa yadda zai yi da ni. 'karshe dai dana gigita masa lissafi shi da kansa ma ya cire wandon da yake ta mayarwa a lokacin da nake so na cire, ya birkitani na kwanta a gadon ya had'a ni da katifar da take shimfide a gadon ya matse sosai yana sakin wani irin nishi da sambatu. Ganin na kamo bakin zaran sai na kara fito da kalolin soyayya da janye hankali na kuwa rikita abuna! ya dinga shassheka dama duk sanda na so naga fitar hawayensa idan muna sunah na san inda zan kamo a take kuwa suka dinga fita da d'an shashheka da gurnani wanda sautin ke fita hade da fitar numfashinsa.
Da safe ya ware sosai. Domin duk taurin kan namiji zai so ace yana samun irin salon da na yi amfani dashi jiya.
Ganin ya saki jikinsa ya daina fushin har muna hira sai hankalina ya kwanta na samu nutsuwar zuciyata. Da kaina kuma na shiga kicin na shirya masa abin kari, kwana biyu Falalu ya huta abincin dare kawai yake yi mana gabad'aya har dashi maigidan.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su

dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*24*
Kin ga dama na gaya miki duk aikin da ake yi akanta bai yi tasiri ba. Kina jin fa irin tsawar da take buga mini kamar itace gaba da ni. Na rantse da Allah da Annabi a yanzu yadda na tsani mutuwata haka na tsaneta, shegiya tsinanniya mutsiyaciya."Hadiza ta kare maganarta cikin ciwon rai dan har da wata 'kwalla a kwarmin idonta.
Ummantasu ta dubeta itama dai cikin takaicin take a sanyaye ta furta." Da jifa zai salwantar da Amina da tun tana cikin uwarta ta nakasa. Babu irin abinda ban yi ba akanta amma tana kafe, abinda ya fi miki kawai ki nuna

mata sadudarki kin yi nadama domin kuwa muddin ki ka ce za ki yi fad'a da ita to kuwa kece a kasa tunda babu abinda ki ka taka mutane da yawa zasu ce hassada kike yi mata."

Cikin k'unar zuciya ta furta." Tunda na je gidanta nake yi mata bauta, na 'kaskantar da kaina na zama kamar baiwarta mussaman a lokacin data haihu amma shine yanzu zata ci mutuncina akan kudin da ba ita ta bayar dasu ba."
Ummantasu ta ja tsaki tana cewa." Ai tunda mijinta ne ya bayar kamar itace ta bayar na gaya miki Hadiza idan ki ka ce zakiyi rigima da ita wallahi kece a kasa, ki bata ha'kuri kawai."
Ta dubeta da takaici ta furta." Umma kece fa ki ka bani goyon bayan yin hakan ta yaya zan fitar dake tunda ta san tare muka had'a kai muka kar'bi kudin.
"Ki barni da ita ni idan ta huce an kwana biyu zan kira ta a waya ni na san abinda zan gaya mata."

Shiru ta yi tana tunani. Ta ce." Ki bi komai a nutse shi ya'ki dan zamba ne, amma ina kara gaya miki yin rigima da ita babbar asara zai janyo mana dani daku tunda kina sane gidan nan kusan duk a hannunta muke Babanku ba sosai yake fita ba duk da ta bashi jarin huluna ganin tana yi masa Aiken kudi akai akai yake yin zamansa a gida.
Hadiza shiru tayi ta rasa abin cewa, yanzu ta fara zargin ummantasu ashe duk kudin da take turowa domin ta je wajan malaminsu akan a daure bakin Amina ba zuwa take yi ba tunda ga abinda take cewa.

Anti Yagana ce ta kira wayar Hadizan kamar yadda ta fada. Ta bude mata wuta sosai dama can basa shiri tana yawan yi mata fad'a dangane da abubuwan da take yi na shashanci tun tana budurwa ta inda take shiga ba tanan take fita ba. Ummantasu ta yi shiru domin dama itama kanwarsu ta bata jikuwa da anti Yaganar. Sai ga Hadiza tana kuka haik'an tana cewa." Anti Yagana kin jima kina nuna mana wariyar launin fata, duk abinda ya danganci Amina kin dinga korarmu kenan ba kya so mu ra'bi inda take sai kace zamu cutar da ita. Dama can kin tsaneni ban san abinda nake yi ba, shi ma Baban namu da ya gaya muku haka bai fahimci yadda ciwon yake ba, amma Fati bata da lafiya kamar yadda na fadawa Aminar gobe ma za mu koma asibitin da ita"
Anti Yagana ta ce." Ai kin iya karya kamar kudin guzuri Hadiza, ni yaushe zan yarda da maganarki gashi saboda baki da mutunci kina karyata Ubanki. Idan kudi kike so ki tambayata mana na san abin duniyarta bai rufe mata Iido ba zata baki sai kawai ku shirya karyar ciwo, itama Fatin da bata da hankali har ta zauna kuke ko'karin dora mata wannan ciwon mai wahalar magani naga wautarta da rashin hankali. Ta numfasa kafin cikin bacin rai ta cigaba da cewa." Wannan ya zama na farko ya kuma zama na karshe wallahi kada ki kuskura ki yi magana da mutumin nan akan ya baku kud'i tunda na lura abin kunya gaba kuka bashi ba baya ba, amma in ba haka ba me zai sanya ku shirya hanyar tsinka mana mutunci a irin wannan gidan, ita kanta 'yar

uwartamu Amina duk ranar da mijin nata ya fahimci k'arya kuka shirya shikkenan girmanta zai ragu a idonsa. Idan wata buk'ata ta taso miki a matsayinki na bazawara ki kira ni ki gaya mini zan yi miki daidai gwargwado ko ki kira ita Aminar ki gaya mata dama kun fi kusa, amna kada ku kara irin wannan haukan."
Maganganun anti Yagana sun yi wa Hadiza zafi mutuka da gaske. Ita anti Yagana haka take idan ranta ya baci duk abinda ya zo bakinta fad'a take ko ka mutu ko kayi rai bai dameta ba.

Cikin kumfar baki da tayar da jijiyar wuya don har sai da Anti Sakina ta fito daga d'akin ta tsaya a dokin kofa jin hayaniya na tashi. Hadiza cigaba da cewa." To anti Yagana da kike cewa duk abinda ya same ni na gaya miki ko an fada miki ni ma haka zan zauna a tsiyace, bari fa ki ji arzikin nan Allah ne yake bayar dashi ba wani d'an iska ba, itama Aminar ai takarsa tayi bata gada a wajan uwa da uba ba. Kuma wanda ta yi kafin aure ai na zina ne wanene bai sani ba, fasikanci tayi tana tallata surar jikinta a duniya wanene ya san iya adadin manyan mutanan da suka nema ta har ta tara dukiyar. Idan lokacina ya yi wallahi daka ke har ita sai kun jira aikin banza aikin......Ai ba ta jira ta kàrasa ba ta kashe wayarta jikinta yana 'bari ta zauna a saman kujera tana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wai Hadiza ce take kiran Amina da karuwa saboda abin duniya.
Ba ta yi mamaki ba domin dama can sun nuna mata kiyayya. Tunda take bata ta'ba nuna bambanci tsakanin 'yan uwanta ba, duk ta daukesu daya da Aminar da suka fito ciki daya. Ko yau Amina ta yi lefi kwatankwacin irin wanda Hadizan ta yi sai ta ci mutuncina wata'kila ma nata ya fi na Hadizan, amma ta girgiza mutuka da gaske da jin wannan furucin daga bakinta..
Ba ta ha'kura ba dai ta kira Fati a waya suka gaisa sosai nan ta fara tambayata yanayin ciwon nata.
Fati ta ce." Typhoid ne ya matsa mini anti wallahi har sai da naje gida akayi mini 'karin ruwa kwanana biyar sannan na dawo. Amma yanzu da sau'ki sosai jikin."
Anti Yagana ta girgiza kai cikin damuwa ta ce.' Allah ya kara sauki Fati ki yi hakuri da yadda kika samu rayuwa kowane bawa akwai kaddarsa ki zauna ki kula da yaranki ki basu tarbiya sosai tunda duk rintse ko babu dad'i mijinki zai baku ku ci to kiyi ha'kuri kada ki yi sha'awar fitowa domin lamarin ba zai miki kyau ba, duk abinda kike buk'ata ki gaya mini ta waya muddin bai fi karfina ba zan yi miki in sha Allahu rabbi."
Cike da jin dadi ta ce." To na gode sosai anti Allah ya saka da alheri. Su kayi sallama bayan ta yi mata al'kawarin tura mata kudi a daran ranar tunda tana da lambar asusunta wanda dama sa'i da lokaci tana yi mata alheri.
Wayarsu da Fati ya tabbatar mata cewa itama bata san abinda Hadizan ta shirya ba wanda har ta jingina mata ciwo. B'angaran ita Fatin din kuwa Hadiza ta bukaci asusunta aro inda ta ce mata mijin Amina ne zai bata jarin Amma ita Fati din bata ganin alert sakamakon matsalar da asusun ya samu sai dai duk sanda aka tura mata kudi a kira ta a gaya mata an tura abu kaza dama ba wani ajiya take yi dashi ba shiyasa ma bata ta'ba transfer ba. Yanzu

ATM din yana hannun Hadiza tana ta zurga-zurgar zuwa banki domin fitar da kudin.

Anti Sakina ta fashe da dariya tana daga tsaye a dokin kofar dakinta ta ce ." Yau dai karshen kumbiya-kumbiya ya kare kunnena ya ji abinda kuke ta boyewa. Ke yanzu don Allah Hadiza ba ki ji kunya ba. Shi fa sharri dan aike ne, duk inda ya je zai dawo. Ki ci ki sha daga taskar Amina amma kike bin ta da kazafi irin na zina. Kin je gidanta kin share watanni kin yi bul bul hakan bai ishe ki ba sai da ki ka damfaro makudan kudi da karyar ciwo, amma saboda 'kin gaskiya kin zo kina kumfar baki wallahi duk wanda ya ce tukunyar wani ba zata tafasa ba tasa ma ko d'umi ba zata yi ba, kun ji kunya daka ke har uwarki kuma wallahi tallahi sai na gayawa babanku abinda kuka yi."
Hadiza cikin fitsara ta ce." To ki gaya masa mana sai me idan kin gaya masa aikin banza da wofi 'yar b'akinciki ai mun fi kusa da ita tunda uba muka had'a ke kuwa fa."
Anti Sakina ta ce." Sakarai kawai haka zakiyi ta zagari a gari tunda zuciyarki bata da kyau."
Ummantasu tana ji suna cacar baki ba tace komai ba, ba kuma ta da niyyar tsawatarwa da Hadizan akan ta yi shiru tunda duk lalacewarta ai matar ubanta ce.
Daga karshe dai anti Sakinar ita ta gaji ta yi shiru hakan ma ya faru ne sakamakon shigowar Usaini shine babban d'anta, ya hanata magana tare da tura ta d'aki ya fito bai kalli inda Hadizan take tsaye ba tana ta zuba ruwan ashariya kamar 'yar maguzawa. Dama basa magana sakamakon yana jin haushin rashin kunyar da takewa babarsu shiyasa kawai ya fita daga harkarta. Saminu ne idan yana gidan bai fita yawon gwangwan d'insa ba yake shigarwa Umman tasu har akwai ranar da ya d'auko dutse irin na wuta daga waje ya saita Hadizan ya jefa mata Allah ya kiyaye ya sauka a gefan kafarta. Ta kama shi da duka kuwa shi kuma yana ta d'ura mata ashariya, da k'yar Ummansu ta kwace shi daga hannunta.

***

Wani irin zaman lafiya muke yi kamar ba sabon ango ba sai wani lallaba ni yake yi yana ji da ni. Ban yi mamaki ba domin duk namijin da zai kara aure indai mai ilimi da hankali ne yakan fito da dabaru domin tausar zuciyar uwar gida. Aka ba ni kudin dannar kirji miliyan sha biyu da kujerar umara. Na dinga godiya kuwa ina ta Tsallen murna sam na ki nuna damuwata duk kuwa da cewa abin yana ta damuna. Na ji dadin kujerar umarar dana samu hankalina zai fi kwanciya idan na dan yi nesa har su gama cin amarcinsu tukkuna. Sahura ta dame ni akan lallai ni ma fa sai na kara gyarawa da muna waya kwanaki na ce mata ni koyaushe a cikin gyara nake ni kaina na sheda ni'ima ta wadace ni. Ina Kuma jimanta yadda zan yi tsayin kwana bakwai ba tare da shi ba domin kuwa Allah ne da kullum duk dare sai mun yi, a wasu lukutan ma har breakfast muke yi kafin na sakko daga samansa nasa shine

kawai idan na tuna yake damuna domin kuwa na yi mugun sabon da zan ji jiki mutuka da gaske.

Inna Uwani tuni ta tafi tunda d'aurin auran ya rage sati daya ta tattara ta tafi bayan ta kwamushi kudi a wajensa, shi dai Allah ya taimakeshi abin duniyarsa bai rufe masa ido ba, gashi bai iya kyauta ba da yawa yake bayarwa.
Yau saura kwana biyu d'aurin aure mai kitso da k'unshi  ta zo har gida ta yi mini ja da baki. Kitson kuwa cewa na yi tayi mini irin na mu na bare bari na gaba tayi mini  tunda ba lefi akwai sumar.
Ya kuwa burge shi sosai saboda rashin abinyi har sai da ya lissafa kitson tamaninin da daya ne. Ni dai dariya kawai nake yi masa. Duk kiran da Hauwa za ta yi masa baya d'agawa a gabana, sai ma ya sanya wayar a jirgi ya share.
Cikin zuciyata na yi ta jin dad'i ganin babu boka babu Malam na kame zuciyar abina wanda ni kad'ai na san sirrin faruwar hakan.
 Wato kishi bala'i ne ban ta'ba gazgatawa ba sai  da maigidan ya kira ni a waya yake tabbatar mini da cewa an dauransa da Hauwa yanzu amma ba zai sake kwana ba komai dare a gida zai dawo.
A lokacin k'irjina  nauyi ya yi mini bayana ya rike ulcerta tana neman tashi wadda tun ina budurwa rabon data motsa mini. Na daure zuciyata sosai domin Ina so na cigaba da nuna masa Ina maraba da zuwan amaryarsa amma har cikin zuciyata na ji dad'in jin ya ce ba zai sake kwana ba, domin kuwa babu abinda ya zo mini a raina da ya gaya mini an dauran auran sai zai iya nemanta tunda ai ta zama mallakinsa.
Cikin 'yar dariya dana kalato na furta." Kai kuwa ranka ya dad'e ka kwana ma gobe da wuri sai ka taso."
Ya furta."A a zan dai dawo domin Ina da damuwa ke kanki kin sani hidimar nan ce ta d'auke mini hankali amma tunda an d'aura alhmdullhi itama gobe zasu kawota......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*

*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*

*07084653262 ko*

*08089965176*

*SIYAN NAGARI!!!!!!*

*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*23*

Bayan tafiyar Hadiza da kwanaki uku sai na ce bari na kira na ji ya taje gida domin na yi mamaki sosai da bata kira ni ba wai bahaushe ya ce 'Idan ka ji shiru lafiya ce.'
Babanmu na fara kira domin mun kwana biyu ba mu gaisa ba. Bayan mun gaisa sosai na tambayashi gida ya ba ni amsa da komai lafiya sai na ji bai sako mini maganar rashin lafiyar Fati ba. Lokaci kan'kani na fara nazarin wani abu a zuciyata.
Na ce." Baba ya jikin Fatin ina fatan  an yi mata aikin domin tun bayan barin Hadiza daga nan nake ta dakon kiran waya domin a sanar da ni halin da take ciki, wallahi hankalina ya tashi sosai da wannan ciwon da ya same ta.
Ya ce." Ai ta ji sauki tuntuni jiya ma ta koma gidanta, maganar aiki kuma ni ban san dashi ba, domin bayanin da mijinta ya yi mini cewa zazzabin typhoid da maleria ne yake damunta. Shine ya kawo ta gida domin a kwance take sosai a can din, k'arin ruwa kawai nasan anyi mata da allurai shikkenan kuma kwana biyu kacal ta warware mijinta ya zo ya d'auketa da yaran suka tafi.
Cike da mamaki da mutuwar jiki na ce." To ikon Allah, amma ni ba haka Hadiza da Ummansu suka gaya mini ba, amma shikkenan babu komai Ubangiji Allah Ya bata lafiya."
Ya amsa da Amin kafin ya d'ora da cewa." Amina me yasa idan kin tashi yin alheri ne ba kya had'awa da Sakina tunda Hadiza ta dawo suke husuma a gidan sun hana ni shan ruwa Hadiza da uwarta sun had'ewa Sakina kai, kuma duk irin alheran da ki ka bata sun hana Umman Saminu, shin ko kema Murja ta lalataki ne."
Da sauri na ce." Wallahi a a Baba, sharrin ba na kowa ba ne face na Hadiza domin kuwa ni duk abinda na bayar gabad'aya gidan na basu ban ware kowa ba, ai kaga ko da salla d'inki iri daya nake yi musu."
Ya sauke ajiyar zuciya yana cewa." Ni ma na zargi Hadiza da d'aga mini hankali, domin kuwa tunda ta kaso auranta ta dawo gida ta zauna shikkenan gidan ya zama kamar sansani, itace fad'a da wannan itace fad'a da wannan."

Na ce." Baba ka yi hakuri kayi mata addu'a Allah ya fito mata da mijin aure, amma ya zama dole na kira ta a waya domin na ji dalilinta na yin hakan."
Ya ce." To shikkenan hakan ya yi Allah ya yi mini albarka."
"Amin Baba zan sanya Hamusu ya tura maka kudi koda da akwai buk'atar da zakayi."
"Na gode sosai Allah ya sanyawa dukiyarki albarka, ya kuma shirya miki zuriarki."

Muna yin sallama na kira Anti Yagana raina a b'ace na shiga sanar da ita abinda Hadiza da Ummansu suka aikata. Yanzu na gane karyar ciwo suka shirya da Fati domin su samu kudi a hannunà ban ta'ba kawo hakan a cikin raina ba domin zaman watannin da ta yi a gidana  ban ta'ba zargin zata cutar da ni ba, don  Ina ganin yadda take shiga damuwa a duk lokacin data gan ni, a cikin matsala.
Anti Yagana itama ranta ya 'baci sosai, ta dinga fad'a tana cewa dama tun farko sai da ta zargi hakan shiyasa a lokacin da ta tubure sai ta zauna mini

ranta bai so ba, babbar damuwarta ma kofar da maigidan ya basu tunda da bakinsa yake cewa idan suna buk'atar wani abu su sanar dashi, wannan zai basu k'warin guiwar zubar mini da dan ragowar mutumcin da nake dashi a wajensa. Ta ce lallai zata kira Hadizan ta ja mata kunne akan abinda suka shirya ba daidai ba ne.

Ni ma a take a lokacin bayan na yi sallama da ita na lalubi lambar Hadizan na kira minti daya ta daga da fara'ata muka gaisa a takaice na ce." Ba na neman wani 'karin bayani daga wajanki Hadiza na gode bisa abinda kuka yi mini, Babanmu ya gaya mini komai, yanzu Hadiza idan kudi kike so a wurina har sai kun shirya karya, me yasa ba zaki tambayeni ba."
Shiru ta yi ba tace komai ba. Na cigaba da cewa." Sannan duk uban kayan nan dana hada da na ci, dana sha, dana sanyawa babu abinda kuka bawa Ummansu Saminu alhalin cewa na yi a rarraba har gidajensu Baba Sule shine kuka had'a gabad'aya babu wanda kuka bawa."
Ba ta ce mini komai ba ta dai yi shiru tana jina. Na ce."Wannan zama na farko ya kuma zama na karshe wallahi tallahi kada ki sake yi mini haka domin ni na tsani na zauna da mutum da zuciya daya amma shi da zuciya dubu yake zaune da ni, kina a matsayin 'yar uwata kina cin dunduniyata ban ji dadin abinda ki ka yi ba wallahi."

"Kin ga Amina ya isa haka don Allah ba za ki kira ni a waya ki nemi gaya mini magana ba, shi ma Babanmu bai san kan ciwon ba shiyasa ya ce miki zazzabi ne, kudi kuma ai ba ke kika bayar ba balle ki ce wani abu, arzikinan fa kema takarsa ki ka yi baki gada ba, don haka baki da bakin yi wa wani gori."
Tsaki na ja na kashe wayata domin idan za mu kwana a haka ba zata damu ba tunda dama mun saba cacar baki tun muna yara. Kuma tun a wancan lokacin take nuna b'akinciki da kishi dangane da dukkanin alherin da zai tunkaro ni.

Bayan kwana uku na samu Hajja domin Ina so na yi magana da Hamusu kuma ina tuna Allah ya isar da ya yi mini. Ban ta'ba kai k'ararsa wurin mahaifiyarsa ba, ba don baya yi mini lefi ba, kawai ina dannewa ne domin zuwa yanzu na saba da kyawawan halayensa da munana. Ban ga dalilin da zai sanya ni a matsi ba bayan shi koyaushe cikin walwala yake wanzuwa mussaman da hidimar auransa take matsowa.

Duk na gaya mata yadda mukayi dashi da Allah ya isan da ya yi mini idan na yi magana da Hamusu. Ta ce." Ki yi hakuri zan yi masa magana, ai kina da gaskiya to me zai sanya a tauyeki bayan abokin kasuwancinki ne, ai ba wata hurd'ar banza kuke yi balle ya nuna kishinsa, ki kyaleshi kada ki sake yi masa maganar ki bar komai a hannuna yau din nan zan yi masa magana."
Na yi mata godiya sosai na tashi jikina da k'wari da karsashi domin na san dole idan ta yi masa magana ya janye abinda ya taka.

A daran ta yi masa maganar kuwa dalilin da ya sa na fahimci hakan canzawarsa domin maganar duniya babu kalar wadda ban yi masa ba ya share ni. Har tu'be kayana na yi a gabansa na tsaya zurr da ni haihuwar uwata bai kalleni balle ya nuna sha'awarsa. Bakam kawai ya yi mini na gama neman maganata na ha'kura domin ganin ban samu dan tayi ba.

Ban d'auki lamarin da zafi ba shiyasa har yanzu na kasa gano dalilin fusatarsa domin ni sai nake ganin wannan lamarin kadai ba zai sanya shi yin wannan gagarimin fushin ba.
Wasa wasa abin yana ta nisa, domin ni na yi zato duk rintsi fushi da gabar da yake da ni ba zai wuce kwana biyu sai gashi yau kwana takawas kenan ba ma ga maciji.
Hankalina ya fara tashi domin gaskiya ban fiye son gaba ba a rayuwata shima kuma na lura ba dabi'arsa ba ce domin da ya fara ma yake watsarwa ya neme ni da shiri, wannan karon kuma ta yi tsanani, ba amsa gaisuwa ba kuma hira balle a kai ga maganar kwanciyar aure.
Na bi duk hanyoyin maslaha domin ganin ya sauke fushinsa amma ya'ki don da ya lura ma abin ya dame ni sai ya kara zage dantse ya yi ta cin magani ya'ki kallona. Ni kuwa a raina nace na san yadda zan yi maka.
Da daddare misalin sha daya da wani abu na hau saman nasa.
Kallo na same shi yana yi a katuwar tv din dake kafe a bedroom din nasa. Na yi mamaki sosai domin kallo bai dame shi ba. Cikin zuciyata na ce rai dangin goro kenan, yau babu lissafi da latsa computer.
Kai tsaye tibin na nufa na kashe na juyo muka had'a ido yana dan hararata amma bai ce mini komai ba.
Na yi murmushi tare da girgiza kaina, hijab din da yake jikina na cire na cillar dashi a gefe na yi tsaye a jikin tibin. A lokacin dana sanya kayan ni kaina sai da kunya ta kama ni, amma nasan wajan wanda zan ni idan ya gan ni dasu lada zan samu.
Kaya ne irin na 'yan iskan turawa wanda basu da maraba da tsirara wandon irin mai igiyar nan ne a gefe da gefe duk ya shige mini tsakani. Rigar kuwa dan mitsitsin soso ne da ya dan rufe saman kirjina amma da ita ma gwara babu tunda duk gasunan sun tullutso waje.
Ina ganinsa da saurin gaske ya d'auke kansa daga barin kallona. Ni kuwa na taho da sassarfa ina rangaji na nufe shi ban tsaya komai ba na fad'a jikinsa na tallefe kansa a kirjina matse shi nayi sosai ina nishi da yin wani irin abu da bakina wanda ba na yin hakan sai muna biyawa juna bukata.
Ya ki'dime ainun! ya fara ko'karin cire ni daga jikinsa yana dan dukan mazaunaina.
Cikin fitar hayyaci murya a sarke na ce." Gaskiya ba zan jure ba, ina cikin bukatarka don haka ka yi mini kawai sai ka cigaba da yin gabar tunda baka jin rarrashi."
Na zira yatsana karami a kunnensa ina yi kamar ina sosa masa.
Da wani irin sauti ya furta." Ni kuma ba ni da wani karsashin da zan yi don ba ni da lafiya ma."

Hannuna yana yawo a sassan jikinsa cikin shgawaba na ce." Ashe kuwa zamu kwana a haka don wallahi ni mai raba ni da kai a yanzu sai Allah." Sautin murmushinsa na ji ya ce." To shikkenan mu kwana a hakan ni ba zan damu ba."
Na dube shi naga yana lumshe Ido na fahimci baya so ya bud'e  naga halin da yake ciki.
A hankali na dan sauka daga jikinsa sai yayi sauri ya bude idon yana kallona da idanunsa da ya fara canzawa.
Kafafunsa naja suka mike sosai yana ta kallona bai ce mini komai ba na zare jallabiyar da take jikinsa na jefar. Komai na jikina na cire sai ya janye idonsa daga gare ni yana sake lumshe idonsa.
Jin ina ko'karin cire gajeran wandon dake jikinsa da sauri ya bud'e idonsa yana fad'in." Ke menene haka?"
Na 'kankance Ido ina fad'in hakkina zan kar'ba."
Dariya ya sa yana jan tsaki ya janye kafarsa yana ko'karin mayar da wandon na ri'ke da kyau.
"Ai ka ce sai dai mu kwana ko? Ni idan zan kwana ma ban damu ba domin yadda nake jin kaina yau na fi zakanya kuzari."
Ya yi mini shiru bai tanka mini ba.
Ko'karin hawa gadon yake yi na bi shi na danne ya yi flat ni kuma ina samansa cikin gaggawa na fara raromo bakinsa. Duk ciccijiewar da ya dinga yi sai da dauriyarsa ta 'kare ya rasa yadda zai yi da ni. 'karshe dai dana gigita masa lissafi shi da kansa ma ya cire wandon da yake ta mayarwa a lokacin da nake so na cire, ya birkitani na kwanta a gadon ya had'a ni da katifar da take shimfide a gadon ya matse sosai yana sakin wani irin nishi da sambatu. Ganin na kamo bakin zaran sai na kara fito da kalolin soyayya da janye hankali na kuwa  rikita abuna! ya dinga shassheka dama duk sanda na so naga fitar hawayensa idan muna sunah na san inda zan kamo a take kuwa suka dinga fita da d'an shashheka da gurnani wanda sautin ke fita hade da fitar numfashinsa.
Da safe ya ware sosai. Domin duk taurin kan namiji zai so ace yana samun irin salon da na yi amfani dashi jiya.
Ganin ya saki jikinsa ya daina fushin har muna hira sai hankalina ya kwanta na samu nutsuwar zuciyata. Da kaina kuma na shiga kicin na shirya masa abin kari, kwana biyu Falalu ya huta abincin dare kawai yake yi mana gabad'aya har dashi maigidan.....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
□□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#

VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*24*
Kin ga dama na gaya miki duk aikin da ake yi akanta bai yi tasiri ba. Kina jin fa irin tsawar da take buga mini kamar itace gaba da ni. Na rantse da Allah da Annabi a yanzu yadda na tsani mutuwata haka na tsaneta, shegiya tsinanniya mutsiyaciya."Hadiza ta kare maganarta cikin ciwon rai dan har da wata 'kwalla a kwarmin idonta.
Ummantasu ta dubeta itama dai cikin takaicin take a sanyaye ta furta." Da jifa zai salwantar da Amina da tun tana cikin uwarta ta nakasa. Babu irin abinda ban yi ba akanta amma tana kafe, abinda ya fi miki kawai ki nuna mata sadudarki kin yi nadama domin kuwa muddin ki ka ce za ki yi fad'a da ita to kuwa kece a kasa tunda babu abinda ki ka taka mutane da yawa zasu ce hassada kike yi mata."

Cikin k'unar zuciya ta furta." Tunda na je gidanta nake yi mata bauta, na 'kaskantar da kaina na zama kamar baiwarta mussaman a lokacin data haihu amma shine yanzu zata ci mutuncina akan kudin da ba ita ta bayar dasu ba."
Ummantasu ta ja tsaki tana cewa." Ai tunda mijinta ne ya bayar kamar itace ta bayar na gaya miki Hadiza idan ki ka ce zakiyi rigima da ita wallahi kece a kasa, ki bata ha'kuri kawai."
Ta dubeta da takaici ta furta." Umma kece fa ki ka bani goyon bayan yin hakan ta yaya zan fitar dake tunda ta san tare muka had'a kai muka kar'bi kudin.
"Ki barni da ita ni idan ta huce an kwana biyu zan kira ta a waya ni na san abinda zan gaya mata."

Shiru ta yi tana tunani. Ta ce." Ki bi komai a nutse shi ya'ki dan zamba ne, amma ina kara gaya miki yin rigima da ita babbar asara zai janyo mana dani daku tunda kina sane gidan nan kusan duk a hannunta muke Babanku ba sosai yake fita ba duk da ta bashi jarin huluna ganin tana yi masa Aiken kudi akai akai yake yin zamansa a gida.
Hadiza shiru tayi ta rasa abin cewa, yanzu ta fara zargin ummantasu ashe duk kudin da take turowa domin ta je wajan malaminsu akan a daure bakin Amina ba zuwa take yi ba tunda ga abinda take cewa.

Anti Yagana ce ta kira wayar Hadizan kamar yadda ta fada. Ta bude mata wuta sosai dama can basa shiri tana yawan yi mata fad'a dangane da abubuwan da take yi na shashanci tun tana budurwa ta inda take shiga ba tanan take fita ba. Ummantasu ta yi shiru domin dama itama kanwarsu ta bata jikuwa da anti Yaganar. Sai ga Hadiza tana kuka haik'an tana cewa." Anti Yagana kin jima kina nuna mana wariyar launin fata, duk abinda ya danganci Amina kin dinga korarmu kenan ba kya so mu ra'bi inda take sai kace zamu

cutar da ita. Dama can kin tsaneni ban san abinda nake yi ba, shi ma Baban namu da ya gaya muku haka bai fahimci yadda ciwon yake ba, amma Fati bata da lafiya kamar yadda na fadawa Aminar gobe ma za mu koma asibitin da ita"
Anti Yagana ta ce." Ai kin iya karya kamar kudin guzuri Hadiza, ni yaushe zan yarda da maganarki gashi saboda baki da mutunci kina karyata Ubanki. Idan kudi kike so ki tambayata mana na san abin duniyarta bai rufe mata Iido ba zata baki sai kawai ku shirya karyar ciwo, itama Fatin da bata da hankali har ta zauna kuke ko'karin dora mata wannan ciwon mai wahalar magani naga wautarta da rashin hankali. Ta numfasa kafin cikin bacin rai ta cigaba da cewa." Wannan ya zama na farko ya kuma zama na karshe wallahi kada ki kuskura ki yi magana da mutumin nan akan ya baku kud'i tunda na lura abin kunya gaba kuka bashi ba baya ba, amma in ba haka ba me zai sanya ku shirya hanyar tsinka mana mutunci a irin wannan gidan, ita kanta 'yar uwartamu Amina duk ranar da mijin nata ya fahimci k'arya kuka shirya shikkenan girmanta zai ragu a idonsa. Idan wata buk'ata ta taso miki a matsayinki na bazawara ki kira ni ki gaya mini zan yi miki daidai gwargwado ko ki kira ita Aminar ki gaya mata dama kun fi kusa, amna kada ku kara irin wannan haukan."
Maganganun anti Yagana sun yi wa Hadiza zafi mutuka da gaske. Ita anti Yagana haka take idan ranta ya baci duk abinda ya zo bakinta fad'a take ko ka mutu ko kayi rai bai dameta ba.

Cikin kumfar baki da tayar da jijiyar wuya don har sai da Anti Sakina ta fito daga d'akin ta tsaya a dokin kofa jin hayaniya na tashi. Hadiza cigaba da cewa." To anti Yagana da kike cewa duk abinda ya same ni na gaya miki ko an fada miki ni ma haka zan zauna a tsiyace, bari fa ki ji arzikin nan Allah ne yake bayar dashi ba wani d'an iska ba, itama Aminar ai takarsa tayi bata gada a wajan uwa da uba ba. Kuma wanda ta yi kafin aure ai na zina ne wanene bai sani ba, fasikanci tayi tana tallata surar jikinta a duniya wanene ya san iya adadin manyan mutanan da suka nema ta har ta tara dukiyar. Idan lokacina ya yi wallahi daka ke har ita sai kun jira aikin banza aikin......Ai ba ta jira ta kàrasa ba ta kashe wayarta jikinta yana 'bari ta zauna a saman kujera tana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wai Hadiza ce take kiran Amina da karuwa saboda abin duniya.
Ba ta yi mamaki ba domin dama can sun nuna mata kiyayya. Tunda take bata ta'ba nuna bambanci tsakanin 'yan uwanta ba, duk ta daukesu daya da Aminar da suka fito ciki daya. Ko yau Amina ta yi lefi kwatankwacin irin wanda Hadizan ta yi sai ta ci mutuncina wata'kila ma nata ya fi na Hadizan, amma ta girgiza mutuka da gaske da jin wannan furucin daga bakinta..
Ba ta ha'kura ba dai ta kira Fati a waya suka gaisa sosai nan ta fara tambayata yanayin ciwon nata.
Fati ta ce." Typhoid ne ya matsa mini anti wallahi har sai da naje gida akayi mini 'karin ruwa kwanana biyar sannan na dawo. Amma yanzu da sau'ki sosai jikin."

Anti Yagana ta girgiza kai cikin damuwa ta ce.' Allah ya kara sauki Fati ki yi hakuri da yadda kika samu rayuwa kowane bawa akwai kaddarsa ki zauna ki kula da yaranki ki basu tarbiya sosai tunda duk rintse ko babu dad'i mijinki zai baku ku ci to kiyi ha'kuri kada ki yi sha'awar fitowa domin lamarin ba zai miki kyau ba, duk abinda kike buk'ata ki gaya mini ta waya muddin bai fi karfina ba zan yi miki in sha Allahu rabbi."
Cike da jin dadi ta ce." To na gode sosai anti Allah ya saka da alheri. Su kayi sallama bayan ta yi mata al'kawarin tura mata kudi a daran ranar tunda tana da lambar asusunta  wanda dama sa'i da lokaci tana yi mata alheri.
Wayarsu da Fati ya tabbatar mata cewa itama bata san abinda Hadizan ta shirya ba wanda har ta jingina mata ciwo. B'angaran ita Fatin din kuwa Hadiza ta bukaci asusunta aro inda ta ce mata mijin Amina ne zai bata jarin Amma ita Fati din bata ganin alert sakamakon matsalar da asusun ya samu sai dai duk sanda aka tura mata kudi a kira ta a gaya mata an tura abu kaza dama ba wani ajiya take yi dashi ba shiyasa ma bata ta'ba transfer ba. Yanzu ATM din yana hannun Hadiza tana ta zurga-zurgar zuwa banki domin fitar da kudin.

Anti Sakina ta fashe da dariya tana daga tsaye a dokin kofar dakinta ta ce ." Yau dai karshen kumbiya-kumbiya ya kare kunnena ya ji abinda kuke ta boyewa. Ke yanzu don Allah Hadiza ba ki ji kunya ba. Shi fa sharri dan aike ne, duk inda ya je zai dawo. Ki ci ki sha daga taskar Amina amma kike bin ta da kazafi irin na zina. Kin je gidanta kin share watanni kin yi bul bul hakan bai ishe ki ba sai da ki ka damfaro makudan kudi da karyar ciwo, amma saboda 'kin gaskiya kin zo kina kumfar baki wallahi duk wanda ya ce tukunyar wani ba zata tafasa ba tasa ma ko d'umi ba zata yi ba, kun ji kunya daka ke har uwarki kuma wallahi tallahi sai na gayawa babanku abinda kuka yi."
Hadiza cikin fitsara ta ce." To ki gaya masa mana sai me idan kin gaya masa aikin banza da wofi 'yar b'akinciki ai mun fi kusa da ita tunda uba muka had'a ke kuwa fa."
Anti Sakina ta ce." Sakarai kawai haka zakiyi ta zagari a gari tunda  zuciyarki bata da kyau."
Ummantasu tana ji suna cacar baki ba tace komai ba, ba kuma ta da niyyar tsawatarwa da Hadizan akan ta yi shiru tunda duk lalacewarta  ai matar ubanta ce.
Daga karshe dai anti Sakinar ita ta gaji ta yi shiru hakan ma ya faru ne sakamakon shigowar Usaini shine babban d'anta, ya hanata magana tare da tura ta d'aki ya fito bai kalli inda Hadizan take tsaye ba tana ta zuba ruwan ashariya kamar 'yar maguzawa. Dama basa magana sakamakon yana jin haushin rashin kunyar da takewa babarsu shiyasa kawai ya fita daga harkarta. Saminu ne idan yana gidan bai fita yawon gwangwan d'insa ba yake shigarwa Umman tasu har akwai ranar da ya d'auko dutse irin na wuta daga waje ya saita Hadizan ya jefa mata Allah ya kiyaye ya sauka a gefan kafarta. Ta kama shi da duka kuwa shi kuma yana ta d'ura mata ashariya, da k'yar Ummansu ta kwace shi daga hannunta.

***
Wani irin zaman lafiya muke yi kamar ba sabon ango ba sai wani lallaba ni yake yi yana ji da ni. Ban yi mamaki ba domin  duk namijin da zai kara aure indai mai ilimi da hankali ne yakan fito da dabaru domin tausar zuciyar uwar gida. Aka ba ni kudin dannar kirji miliyan sha biyu da kujerar umara. Na dinga godiya kuwa ina ta Tsallen murna sam na ki nuna damuwata duk kuwa da cewa abin yana ta damuna. Na ji dadin kujerar umarar dana samu hankalina zai fi kwanciya idan na dan yi nesa har su gama cin amarcinsu tukkuna. Sahura ta dame ni akan lallai ni ma fa sai na kara gyarawa da muna waya kwanaki na ce mata ni koyaushe a cikin gyara nake ni kaina na sheda ni'ima ta wadace ni. Ina Kuma jimanta yadda zan yi tsayin kwana bakwai ba tare da shi ba domin kuwa Allah ne da kullum duk dare sai mun yi, a wasu lukutan ma har breakfast muke yi kafin na sakko daga samansa nasa shine kawai idan na tuna yake damuna domin kuwa na yi mugun sabon da zan ji jiki mutuka da gaske.

Inna Uwani tuni ta tafi tunda d'aurin auran ya rage sati daya ta tattara ta tafi bayan ta kwamushi kudi a wajensa, shi dai Allah ya taimakeshi abin duniyarsa bai rufe masa ido ba, gashi bai iya kyauta ba da yawa yake bayarwa.
Yau saura kwana biyu d'aurin aure mai kitso da k'unshi  ta zo har gida ta yi mini ja da baki. Kitson kuwa cewa na yi tayi mini irin na mu na bare bari na gaba tayi mini  tunda ba lefi akwai sumar.
Ya kuwa burge shi sosai saboda rashin abinyi har sai da ya lissafa kitson tamaninin da daya ne. Ni dai dariya kawai nake yi masa. Duk kiran da Hauwa za ta yi masa baya d'agawa a gabana, sai ma ya sanya wayar a jirgi ya share.
Cikin zuciyata na yi ta jin dad'i ganin babu boka babu Malam na kame zuciyar abina wanda ni kad'ai na san sirrin faruwar hakan.
 Wato kishi bala'i ne ban ta'ba gazgatawa ba sai  da maigidan ya kira ni a waya yake tabbatar mini da cewa an dauransa da Hauwa yanzu amma ba zai sake kwana ba komai dare a gida zai dawo.
A lokacin k'irjina  nauyi ya yi mini bayana ya rike ulcerta tana neman tashi wadda tun ina budurwa rabon data motsa mini. Na daure zuciyata sosai domin Ina so na cigaba da nuna masa Ina maraba da zuwan amaryarsa amma har cikin zuciyata na ji dad'in jin ya ce ba zai sake kwana ba, domin kuwa babu abinda ya zo mini a raina da ya gaya mini an dauran auran sai zai iya nemanta tunda ai ta zama mallakinsa.
Cikin 'yar dariya dana kalato na furta." Kai kuwa ranka ya dad'e ka kwana ma gobe da wuri sai ka taso."
Ya furta."A a zan dai dawo domin Ina da damuwa ke kanki kin sani hidimar nan ce ta d'auke mini hankali amma tunda an d'aura alhmdullhi itama gobe zasu kawota......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*25*

A shagwa'be na ce." Mutumin da yake da sabuwar amarya shine yake cikin damuwa, gaskiya ban yarda ba dadin baki ne."
Murmushi ya yi tare da cewa. Za ki gayawa 'yan garinku ai."
Na ce." Baba ina Hajja ne ka gaya mata na yi kewarta Yusi kuma bana nemansa tunda ya manta da ni."
Yana dariya yake ce wa." Hajja na can wurin 'yan uwanta Yusi kuwa yanzu ya tashi ya fita zuwa wurin abokansa kin san shi da saurin sabo ya samu abokai anan din ."

Sai na tsinci kaina da cewa. " Amma tare zaku dawo?" Gabad'aya hankalina ne bai kwanta ba nasan family dinsu babu mai kaunata sai shi sai mahaifiyarsa da 'yar uwarsa Hajiya Saratu mai sunan mamana. Dalilin da ya sanya ma kenan na'ki binsa a lokacin da zai tafi babu irin rarrashin da bai yi mini ba na ce a a bana zuwa.
Ya ce." Ai ba tare muka tafi ba kin ga da kunya na je na cewa Hajja ta ba ni shi mu tafi ko."
A sanyaye na ce." Hakane kuma."
Kamar ya fahimci abinda yake cikin raina sai ya ce." Ki yi hakuri babu abinda zai same shi in sha Allahu rabbi."
Da sauri na ce ." Ai ban ce dama wani abin zai same shi ba baba, yanzu me kake so ka ci?"
Duk abinda ki ka yi mini zan ci, ina da yin sallar la'asar zan taso in sha Allahu."
Na ce." To shikkenan Allah Ya tsare sai ka dawo."
Cike da karsashi da kwarin gwiwa na ajiye wayar ban tsaya jinkiri ba na fara had'a abinda zan sha domin rikita masa lissafi....08089965176 Muna da ingantattun magunguñan mata masu masifar rikita maigida.
Na shirya masa towo miyar ku'bewa domin shi ma'abocin cin abincin gargajiya ne baya rabo da shan farau farau da dumame! shiyasa nake ajiye masa da safe na d'umama kafin ya fita ya ci.

Gidan ya yi mini girma sosai domin ni ka'dai na kwana da rana ne nake jin karakainar masu aiki magariba kuwa tana yi na shiga d'aki na rufe don ma gidan cike yake da masu tsaro shiyasa na dan samu sasaauci.

Na san dai tunda jirgi ya biyo  ba zai wuce takwas na dare ba ya sauka, amma abin mamaki sai gashi har wajan goma da wani abu babu alamanunsa, na d'auki wayata domin kiransa na ji lafiya a kashe duka layukansa basa shiga. Ban kawo komai ba a raina ba, amma na fi tunanin ko bai samu tashi da wuri ba. Bashi da jirgi na kansa amma yana da alfarma dalilin matsayinsa da kowane lokaci zai iya tasowa.

Sha biyu na dare tana bugawa na fitar da raina da dawowarsa, raina a k'untacce na k'ara lalubar lambobin wayarsa har yanzu a kashe suke basa shiga. Lokaci guda zuciyata ta fara yi mini sa'ke-sake akan canza shawara ya yi kenan bayan ya sanya ni yi masa abinci har da shan maganin mata shine zai kashe wayarsa ba ma zai kira ni ya gaya mini dalilinsa ba.
Na kwanta ina ta juyi marata ta dame ni da ciwo sai had'e cinyata nake yi ina mi'ka tsabar bu'katuwa tabbas dana san ba zai dawo ba da ban sha komai ba.
Da 'kyar bacci ya d'auke ni mara dad'i da armashi don haka kiran sallar farko na tashi  sai da nayi wanka tukkuna na d'aura alwala na fito.
Ina idar da salla na sake lalubar wayarsa is switchup, cike da tsantsar takaici da b'acin rai na ajiye wayar na koma gado na kwanta ina ha'de jikina domin har yanzu a dame nake dama idan nasha hadin yakan yi sati a ko kwana biyar bai daina aiki ba. Hawaye suka zubo mini nasa hannu na goge ina ayyanawa a raina wata'kila ita ta hana shi dawowa, ai dama an ce amarya ko ta buzuzuce sai an yi d'okinta, 'karin takaicina ma da ya kashe wayoyinsa tabbacin baya buk'atar a dame shi da bakinsa ya fad'a yana da damuwa kuma na san ko ta mecece babu yadda za a yi ya ga amarya a kusa dashi bai ta'ba ta ba.

Sai wuraran bakwai da wani abu ya kira ni. Da kamar kada na d'auki wayar saboda yadda nake jin haushin abinda ya yi mini.
Na daga a can kasan makoshi na ce." Ina kwana?"
Da sauri ya amsa yana cewa." Allah Ya taimake ki na yi lefi ko?"
Cikin dauriya na ce." Lefin me?"
"Jiya mun yi dake zan dawo ban samu tahowa ba saboda inna Uwani ta ce mini na tsaya kawai mu taho tare da amaryar tana sallama da 'yan uwa ne, shine dalilin da ya sanya ki ka ji shiru."

A nutse na ce." Shine dalilin kashe waya ko? Ai ka bugu ka gaya mini halin da ake ciki." Babu wata damuwa a tare dashi ya furta." Na yi lefi ki yi hakuri, na kashe wayar ne saboda ina buk'atar hutu don wallahi kin ji na rantse miki sallar Isha'i ma sai da tsakiyar dare dana farka na yi ta, domin bacci ne mai nauyi ya d'auke ni."
"Humm! kawai na ce domin har yanzu ban yarda da abinda ya fad'a ba.

Ya cigaba da cewa." Ni na kammala shiryawa tsaf ita nake jira kin san shirinku na mata, tare ma za mu taho gabad'aya harda Hajja wai ta fasa zama."
Na daure zuciyata na ce." To Allah Ya kawo ku lafiya, na d'umama maka towonka ko?"
"Ki d'umama mini idan mun sauka zan ci in sha Allahu."
"Shikkenan to sai kun dawo." Na kashe wayar ban jira ya sake cewa komai ba, domin duk bin k'wakwkwafina ya'ki ya nuna mini yana zumudin amaryarsa wanda ni Kuma zan kafa masa hujja da hakan. Kishi ma sai ya dinga sanya ni wasi wasi ina tunanin wata'kila ma tana zaune a kusa dashi ya kira ni yake tsarana ni da dadin baki.

Ina aiki abin yana cigaba da damuna a zuciya gabad'aya a rikice nake don tunda nasha maganin nan jiya nake cikin matsananciyar sha'awa, abin ya hadu ne da jin dadi da kuma adadin shekarun na da nake a yanzu ina kan gàniyar buk'ata, bayan haka kuma ya yi mini mugun sabon da mutukar bai kasance ni ba a kullum zan iya shiga wani haliin. Falalu na kira domin ya cigaba da abinda na fara don yanayin jikina ba zai barni na ayi abu daidai ba.

Wannan littafin na kudi ne sister kada ki karanta mini shi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ina wanka ina tunanin halin da zan kasance tunda dole dai na ha'kura dashi tsayin sati tunda budurwa ce abinda musulunci ya bata kenan. Ban san yadda zan yi ba don gaskiya ba abinda nake buk'ata sai namiji a cikin yanayin da nake ci.
Sai wajan uku na rana suka sauka.
Ban yarda yanayin da nake ciki ya sanya mini nawa da kasala ba balle wani daga cikinsu ya ga kamar kishi ne.
Na tar'be su da fara'a har ita amaryar da samu kujera ta 'kame ta ci uban gayu kamar wadda zata je gasar sarauniyar kyau harda alkyabba. Shi bai tsaya ba kaitsaye samansa ya nufa domin kallo d'aya na yi masa na fahimci akwai gajiya a tare dashi.
a daidai lokacin dana fito daga kicin da tire a hannuna na ji tana ce mata "Ai ni ma tafiya zan yi, dama dalilin zamana goyon cikin Amina ne to ta haihu Allah ya tabbatar da aurenki da Tajo zaman me zan yi kuma, Ina dai kara gaya miki kada na ji kada na gani Hauwa nasan halin kowa daga cikinku don Allah ku zauna lafiya."

A nutse na ajiye Tiran abincin na ce." Haba Hajja ya na ji kina fad'in tafiya za ki yi, ki yi zamanki mana."
Ta girgiza kai tana ko'karin d'aukar gorar ruwa na d'auka na bude mata ta furta." Gwara na tafi Amina ai daka ke har ita Hauwan ba yara ba ne na san ba za ku ba ni kunya ba."

Cikin nutsuwa na ce." In sha Allahu rabbi Hajja."
Ta ajiye gorar ruwan bayan ta 'kurba a nutse ta ce." Dama ba ni da matsala dake Amina tunda zama ya had'a ni na ga halinki, itama Hauwa haihuwarta ne kawai ban yi ba kowa yana da dabi'a mai kyau a cikinku, don haka don Allah ku ri'ke amanar junanku, ku zauna lafiya kada ku yarda ma'kiya su ji halin da kuke ciki."
A daidai lokacin da take wannan maganar ya sauko daga saman yana waya ya yi wanka yana sanye cikin farar jallabiya idonsa da gilashinsa as'usul.
Ya zauna kusa da Hajja Yana cigaba da wayar da yake yi.
Duk muka yi shiru domin yanayin yadda yake fad'a a wayar shi zai tabbatar maka da cewa akwai matsala.
"Me yasa baka sanar da ni tuntuni ba sai yanzu da kake gudun kada asirinka ya tuno shine ka kira ni kake ko'karin kare kanka, ban yarda da kai ba Isiyaku bakinku daya da Sammani, kuma wallahi tallahi idan na yi bincike na tabbatar da gaskiyar abinda kuka aikata ran kowa sai ya baci a cikinku."
Ya kashe wayar bai saurari abinda yake  cewa ba. Hajja ta ce." Wani abin ne ya faru kuma?"
Babu sukuni a tare dashi ya ce.'' Hajja ki dubi tsayin shekarun da nayi da Sammani amma yau an wayi gari yana daya daga cikin mutanan da suke kokarin kai ni kasa tare da janyo mini zagi a duniya."
Ya gyada kai cikin damuwa ta ce.'' Sammanin kuma me ya yi maka, ka yi bincike sosai kada ka yanke hukunci cikin rashin sani, Ina ganin Sammani ba zai cutar da kai ba.
Murmushi kawai ya yi ya ce." Hajja kenan, mutum fa ya kan iya canza hali a wasu lokotan saboda wasu dalilai amma yanzu ace kamar Sammani da na d'auki ragamar kula mini da harkokina na bashi shine zai dinga danne ha'kokin mutane ya gina kansa da gumin marayu. Kwanaki ya kira ni yake gaya mini rasuwar wani ma'aikacinmu, a ka'ida ne daman duk wanda yake aiki a 'karkashina namiji ko mace ya rasu na kan fitar da kudi masu kauri na bawa magana, ko kuma idan ina buk'atar sabbin ma'aikata zan sallami wad'anda karfinsu ya kare na kuma basu jari domin su juya dan cigaba da kula da iyalinsu. Lokacin da ya sanar da ni rasuwar 'Dayyabu Haruna jajirtacen ma'aikaci na ne wanda kwazonsa ma ya sanya muke shiri sosai  na fitar da kud'i miliyar biyar na wakilita shi Sammanin kamar koyaushe ya je gidan marigayin ya yi ta'aziya a madadina ya kuma basu wannan kud'i dana bayar ashe sai ya sanya a lalitarsa, sai yanzu  ake sanar da ni iyalan marigayin sun shiga gidan redio suna koke-koke tare da aibata, jarida har ta fita yanzu haka."
Sukairaju daya daga cikin escot d'insa ya shigo da jaridu biyu a hannunsa. Tun kafin ya k'araso wurin da muke yake fad'in." Kin gani ko, Hajja kin ga maganar da nake miki."
Sukairaju ya rusina tare da mika masa da sauri ya kama hanyar fita ba tare da ya ce komai.

Ni kam idona kansa a lokacin da yake duba jaridun ransa a tsananin b'ace don sai na ce ma  wannan shine karo na biyu da naga tsananin fushinsa na

farko lokacin da na kai k'ararsa wurin Hajja na biyu kuma wannan abin da ya faru.
Jiki a mace na yi kasa da kaina kwalla ta ciko idonsa ashe zargin mutumin nan kawai nake yi da farko ban fahimceshi ba, da gaskiyar wannan matar da muka ta'ba haduwa a daidaita sahu inda take cewa duk ma'aikacin da ya mutu a karkashin kamfaninsa yana taimakawa iyalinsa. Hawayen suka zubo nasa hannu da sauri na goge domin Yaya Aminu ne ya fado mini a cikin raina.
Ya duba duk wajan da sunansa ya fito ya kuma duba hoton yaran mamacin hadda mayafiyarsu tana kuka. Ransa ya sake b'aci ya dubi Hajja cikin damuwa ya furta." Yanzu idan Sammani bai taimakawa wad'annan bayin Allan ba ai bai kamaci ya take musu hakkinsu ba, ban ji ciwon maganganun da suka yi akaina ba abinda ya daga mini hankali yadda shi Sammanin yake zambatata, menene bai mallaka ba a karkashina, shi kansa yanzu yana da halin da zai taimakawa mutane saboda damar da na bashi Allah ya bashi, amma na san abinda zan yi masa."
Hajja a sanyaye ta ce." Hakika Sammani ya yi mini bazata kuma ban ta'ba tunanin zai aikata hakan ba, amma ka yi hakuri ka ji ko, ai ka saba d'aukar irin wannan matsaltsalun ba tun yau ba, ka yi masa hukunci daidai gwargwado amma kada ya yi tsanani, Allah ya yi n
Maka albarka, ya kara tsare mini kai."
Gabad'aya muka amsa har da amarya.
Ya dube ni yna cewa." Ki kawo mini dumaman towon nan."
Na amsa tare da tashi a nutse na nufi kicin din ina fitowa ya ce ki kai mini sama sai ki zo ina da magana daku."
Ba tare da nace komai ba na nufi saman nasa da kayan abincin hannuna.
Lokacin dana sauko Hajja ta shiga d'aki domin hud'u saura a lokacin na san salla za ta yi....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH*
☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da

shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

*26*
Su biyu na samu a zaune suna dan magana 'kasa-'kasa. Na kàrasa na zauna wurin da na tashi ina dan jin  wani abu a cikin raina.

Ya dube ni a nutse kafin ya furta." Na san dai duk wata nasiha Hajja ta yi muku, ke Hauwa tun muna can na ji anata yi miki fad'a da nasiha kala kala akan aure da kuma ha'kuri da juriya. Ban cika son fitina ba dalilin ma da ya sanya kenan nake ji a raina zan iya kare rayuwata tare daku biyu rak muddin kuka samar mini da farinciki. Amina ga kanwarki nan Hauwa dukda ta girmeki da shekaru amma yanzu a matsayin k'anwa take a wurinki don Allah na baki amanarta."
Da sauri na dube shi jin yana had'a ni da Allah wannan mai wankakken idon zai ba ni amana. Na mayar da kaina kasa ban ce komai ba ya cigaba da maganganunsa wasu akan ka'ida wasu kuwa sun sa'ba da tunanina kamar dai amanar da yace ya ba ni, ban kar'ba kuma zan gaya masa hakan domin wani abu ba zai faru ba ya zo ya tuhume ni a kan wane dalili matar da ta girme ni ta fini gogewa da ilimin boko zai ba ni amana.
Ita kuwa sai gyada kanta take yi tana murmushi tare da cewa." To shikkenan in sha Allahu, duk abinda ya fad'a sai ta ce. "To za a kiyaye."
Ya ce." To ke ban ji kin ce komai ba."
A nutse na ce." Ni ma na yi alkawari in sha Allahu za mu zauna lafiya, kai kuma Allah ya baka ikon yin adalci a tsakaninmu."
Ya ji dad'in lafazina sosai kuwa. Ya dubeta Yana fad'in." Sukairaju ya shigo miki da kayanki ko?"
Ta ce." E ya ajiye su a wancan d'akin." Ta fad'a tana nuna d'akin da yake kallon nawa."
Sai ya ce." To babu lefi hakan duk dai mai girkin zata same ni a samana." Ta d'an gyara zama da wani kyataccen murmushi a fuskarta tana kashe masa ido ta ce." My na ce ko dai zaka ba ni waje a saman naka kasan ina da matsalar ciwon kirji bana iya zurga zurgar
hawa bene ko a wajan aiki ne idan na tsananta sai ciwona ya tashi, Ina ganin idan ba damuwa ka ba ni d'aki a kusa da kai zai fi mini sauki."
Sai ya ce." A don wannan ai mai sau'ki ne Hauwa sai ki hau ki duba wanda ya yi miki babu matsala." Ya fad'a yana d'an duban inda nake zaune."
Yanayina bai canza ba sai dai na tafi tunanin manufarta na son zama a kusa dashi don ban yarda da abinda tace ba wata'kila akwai wani abu a cikin ranta.
Ni ba zan yi abinda ta yi ba balle tace ina gasa da ita, ina da 'kiba ina buk'atar motsa jiki babu wani sama da zan hau don ganinta a can, amma ya zame mini dole na zuba ido sosai a kansu gabad'aya.
 Ganin yana waya da Sukairaju akan sha'anin matarsa ya sanya na tashi ba tare da na ce komai ba na nufi d'akina na bar su a wurin.
Mintina goma sha biyar Yusi ya shigo lokacin ina gyara jeran madubina na dube shi a nutse na ce." Yusi idonka kenan baka nema na, ka manta da ni ko?"
Ya rungume ni yana yana dariya yana cewa." Mama kece fa kika ce duk lokacin da na ganku a falo kuna zaune na daina zuwa wurin."
Na gyad'a kai Ina cewa." E haka na ce, amma me yasa da kuka dawo baka neme ni ba, ai ka zo mu gaisa ko?"

Ya rike hannuna yana fad'in ." To ki yi hakuri." Ban ce komai ba na cigaba da gyara kayan shafata sai yasa hannu yana taya ni. Ya ce." Mama nasan yanzu Yayana ya kara girma ko?"
Na ce." Sosai ma, ai za mu sake komawa duba shi in sha Allah." Da murna a tare dashi ya ce." To shikkenan mama, amma yaushe zai gama karatun kuma idan an sallamo shi daga makarantar a ina zai zauna."
Na dube shi a nutse na furta." A can wajan Gwaggwo mana, mun yi magana da Hamusu zai dinga tafiya dashi kasuwa."
Wannan maganar na yi ta ne a daidai lokacin da maigidan ya turo kofar d'akin a bazata don ban yi tsammanin hakan ba ya shigo. Yana da kaifin ji dalilin da ya sanya ma kenan ban tsaya yin kokwanto akan ya ji ko bai ji ba.
Kawai na zuba masa ido yayin da shima ya zuba mini nasa idon wanda suke cike da tuhuma da zargi. Na fahimci yanzu yadda ya tsani mutuwarsa haka ya tsani jin sunan Hamusu a bakina, ban san menene dalilin da ya sanya ya d'ora masa karan tsana ba, bayan ada ba haka yake ba.
Yusi ya bashi hannu suka cafka dama sararsu kenan motsi kad'an sai su had'a hannu. Ya dafa kansa da cewa." Ka je d'akina na rage maka abinci." Sai ya sake bashi hannu a karo na biyu suka tafa.
Ya kama hanya da sauri ya bude d'akin ya fita. Ya rage da gani sai shi a d'akin. Na nemi gefan gado na zauna ina kallonsa don ban san da mai ya shigo ba, na san dai tunda ya ji maganar Hamusu ba zai yi shiru ba. A cikin halayensa marasa kyau akwai zargi na gama fahimtarsa.

Na gyara yanayin fuskata sosai domin tarar abinda yake bakinsa. Ya zauna a gefana yana fad'in.'' Wace magana na ji kuna tattaunawa da Yusuf yanzu dai shine abokin shawararki ko?"

Murmushin takaici na yi na ce." A a kai ne abokin shawarata Baba, magana muke yi akan Kamalu yana tambayata idan ya dawo daga makaranta a Ina zai zauna na ce masa can wurin kakarsu Gwaggo  mun yi magana da Hamusu zai dinga tafiya dashi kasuwa."

Ya gyada kansa yana dubana ya furta." Ashe kina bibiyar sha'anin yaron."
Cike da mamaki na ce sosai ma kuwa." Ya furta." Babu inda zai zauna sai nan tare da mu gabad'aya domin raba kan yaran zumuncinsu zai yi rauni, baya ga haka kuma, a can unguwar taku ya lalace ai, to me zai sanya kuma a sake mayar dashi, idan har kun yanke shawarar zamansa a can kano to  sai ku had'a da d'an'uwansa gabad'aya ku ajiyesu a waje daya."

Na yi shiru ina auna maganarsa. Gabad'aya kaina ya kulle na gaza fahimtar abinda yake nufi da wannan maganganun yanzu ina iya furta wata magana ya canza mini manufa, ni dashi duka ba mu da karfin iko kamar dangin Babansu. Hamusu kuma yana iyakacin bakin kokarinsa wajan ganin ya bashi girma kuma bashi da wata matsala, amma tunda sun nema kuma suna da hakki akan yaran nan ya kamata a ce wannan karon na yi kawaici da alkunya

na ba su daya na rike d'aya, amma ina ganin ba zan samu goyon bayansa ba, nema ma yake ya mayar da abin rigima da 'bangaranci.
Na share shi kawai ban ce masa komai ba domin ina danne zuciyata ne ba na son na biye masa na san idan muka fara ni dashi gabad'aya ba zata yi mana kyau ba."
Ya tashi zai fita na ce." A game da maganarka ta d'azu ina da ja kai."
Ya tsaya tare da juyowa yana kallona.
"Wace magana kenan."
"Dangane da amanar matarka da ka ce ka ba ni, ban kar'ba gaskiya domin ni ma nema nake yi ka ri'ke amanata don har yanzu ban san kaina ba."
Ya ce." Ai hakkinki ne a matsayinki na babba ki ri'ke mini amanar gida da duk wanda na kawo na ajiye shiyasa na gaya miki."
Na ce." Ban kar'ba ba gaskiya kuma zuciyata ba ta aminta da zamanta a samanka ba, idan adalci za ka yi kawai ka ce mata ta sauko kasa."
A nutse ya furta." Ba ki ji uzurinta ba ne, tana da ciwon kirji ta ce ko a wajan aiki a kasa take ba ta iya zurga-zurgar hawa sama."
D'auke kaina na yi ban ce masa komai ba. Ya ce." Idan kina ganin da damuwa to kema sai ki tattaro ki hawo saman ku tare bakidaya hakan zai fi."
"Ina buk'atar tsinka jinina, da zan hau ai da tun kafin ta zo gidan na hau."
Ya daga kafad'arsa ba tare da ya ce mini komai ba ya bud'e kofa ya fita.
Na ja jiki ahankali na kwanta saman gado ina matse jikina kawai na ji hawaye na fita daga idona.
Ajiyar zuciya na sauke tare da dan rintse ido yayin da damuwa ke sake sukar ilahirin jikina.
Daurewa kawai nake yi  ganinsa ya k'ara motsa mini bukatarsa da ta dame ni.
 Haka na 'kàrasa yini na cikin damuwa da takura da daddare da kyar na fita falon shi ma don kada Hajja ta zargi wani abin ne, na same su kuwa gabad'aya har ita amaryar inda ta sheka ado da wani uban Les ta soka d'aurin dankwali wanda ya fito da k'arin gashin da ta yi. Kwaliyya ta yi sosai irin ta amare har dasu gashin ido ga sarka nan d'azu awarwaro da zubona a yatsun hannunta.
Ban damu ba domin abin da ya dame ni daban shiyasa adonta bai d'auke mini hankali ba, abinda dai ya so ya bata mini rai bai wuce ganinsa zaune a saitinta ba suna magana da juna.
Na yi 'kokari sosai wajan nuna ban san me suke yi ba, muka gaisa har shi din da yake dan satar kallona itama amaryar ta yi mini sannu da fitowa Hajja tana cewa" ai yanzu nake shirin aika Yusi ya kiraki."  Na ce." Wallahi ina yin sallar magriba bacci ya kwashe ni sai yanzu na farka.
Kafin tayi magana aka kira shi a waya maganarsa ta d'auki hankalinmu gabad'aya zance ne dai bai mutu ba domin iyalan wani mamacin ma sun sake yin magana a sahar nan ta fece book inda suma suke kalubalantarsa akan take hakkinsu da ya yi.
Gidan jaridar da duniya ta aminta da rahotanninsu sune suka kira shi domin neman k'arin bayani da kuma neman alfarma samun lokaci daga wajensa don su tattauna ya kuma wanke kansa dangane da zargin da jama'a suke yi

a kansa.Su biyu na samu a zaune suna dan magana 'kasa-'kasa. Na kàrasa na zauna wurin da na tashi ina dan jin  wani abu a cikin raina.
Ya dube ni a nutse kafin ya furta." Na san dai duk wata nasiha Hajja ta yi muku, ke Hauwa tun muna can na ji anata yi miki fad'a da nasiha kala kala akan aure da kuma ha'kuri da juriya. Ban cika son fitina ba dalilin ma da ya sanya kenan nake ji a raina zan iya kare rayuwata tare daku biyu rak muddin kuka samar mini da farinciki. Amina ga kanwarki nan Hauwa dukda ta girmeki da shekaru amma yanzu a matsayin k'anwa take a wurinki don Allah na baki amanarta."
Da sauri na dube shi jin yana had'a ni da Allah wannan mai wankakken idon zai ba ni amana.  Na mayar da kaina kasa ban ce komai ba ya cigaba da maganganunsa wasu akan ka'ida wasu kuwa sun sa'ba da tunanina kamar dai amanar da yace ya ba ni, ban kar'ba kuma zan gaya masa hakan domin wani abu ba zai faru ba ya zo ya tuhume ni a kan wane dalili matar da ta girme ni ta fini gogewa da ilimin boko zai ba ni amana.
Ita kuwa sai gyada kanta take yi tana murmushi tare da cewa." To shikkenan in sha Allahu, duk abinda ya fad'a sai ta ce. "To za a kiyaye."
Ya ce." To ke ban ji kin ce komai ba."
A nutse na ce." Ni ma na yi alkawari in sha Allahu za mu zauna lafiya, kai kuma Allah ya baka ikon yin adalci a tsakaninmu."
Ya ji dad'in lafazina sosai kuwa. Ya dubeta Yana fad'in." Sukairaju ya shigo miki da kayanki ko?"
Ta ce." E ya ajiye su a wancan d'akin." Ta fad'a tana nuna d'akin da yake kallon nawa."
Sai ya ce." To babu lefi hakan duk dai mai girkin zata same ni a samana." Ta d'an gyara zama da wani kyataccen murmushi a fuskarta tana kashe masa ido ta ce." My na ce ko dai zaka ba ni waje a saman naka kasan ina da matsalar ciwon kirji bana iya zurga zurgar
hawa bene ko a wajan aiki ne idan na tsananta sai ciwona ya tashi, Ina ganin idan ba damuwa ka ba ni d'aki a kusa da kai zai fi mini sauki."
Sai ya ce." A don wannan ai mai sau'ki ne Hauwa sai ki hau ki duba wanda ya yi miki babu matsala." Ya fad'a yana d'an duban inda nake zaune."
Yanayina bai canza ba sai dai na tafi tunanin manufarta na son zama a kusa dashi don ban yarda da abinda tace ba wata'kila akwai wani abu a cikin ranta.
Ni ba zan yi abinda ta yi ba balle tace ina gasa da ita, ina da 'kiba ina buk'atar motsa jiki babu wani sama da zan hau don ganinta a can, amma ya zame mini dole na zuba ido sosai a kansu gabad'aya.
Ganin yana waya da Sukairaju akan sha'anin matarsa ya sanya na tashi ba tare da na ce komai ba na nufi d'akina na bar su a wurin.
Mintina goma sha biyar Yusi ya shigo lokacin ina gyara jeran madubina na dube shi a nutse na ce." Yusi idonka kenan baka nema na, ka manta da ni ko?"
Ya rungume ni yana yana dariya yana cewa." Mama kece fa kika ce duk lokacin da na ganku a falo kuna zaune na daina zuwa wurin."

Na gyad'a kai Ina cewa." E haka na ce, amma me yasa da kuka dawo baka neme ni ba, ai ka zo mu gaisa ko?"
Ya rike hannuna yana fad'in ." To ki yi hakuri." Ban ce komai ba na cigaba da gyara kayan shafata sai yasa hannu yana taya ni. Ya ce." Mama nasan yanzu Yayana ya kara girma ko?"
Na ce." Sosai ma, ai za mu sake komawa duba shi in sha Allah." Da murna a tare dashi ya ce." To shikkenan mama, amma yaushe zai gama karatun kuma idan an sallamo shi daga makarantar a ina zai zauna."
Na dube shi a nutse na furta." A can wajan Gwaggwo mana, mun yi magana da Hamusu zai dinga tafiya dashi kasuwa."
Wannan maganar na yi ta ne a daidai lokacin da maigidan ya turo kofar d'akin a bazata don ban yi tsammanin hakan ba ya shigo. Yana da kaifin ji dalilin da ya sanya ma kenan ban tsaya yin kokwanto akan ya ji ko bai ji ba.
Kawai na zuba masa ido yayin da shima ya zuba mini nasa idon wanda suke cike da tuhuma da zargi. Na fahimci yanzu yadda ya tsani mutuwarsa haka ya tsani jin sunan Hamusu a bakina, ban san menene dalilin da ya sanya ya d'ora masa karan tsana ba, bayan ada ba haka yake ba.
Yusi ya bashi hannu suka cafka dama sararsu kenan motsi kad'an sai su had'a hannu. Ya dafa kansa da cewa." Ka je d'akina na rage maka abinci." Sai ya sake bashi hannu a karo na biyu suka tafa.
Ya kama hanya da sauri ya bude d'akin ya fita. Ya rage da gani sai shi a d'akin. Na nemi gefan gado na zauna ina kallonsa don ban san da mai ya shigo ba, na san dai tunda ya ji maganar Hamusu ba zai yi shiru ba. A cikin halayensa marasa kyau akwai zargi na gama fahimtarsa.

Na gyara yanayin fuskata sosai domin tarar abinda yake bakinsa. Ya zauna a gefana yana fad'in.'' Wace magana na ji kuna tattaunawa da Yusuf yanzu dai shine abokin shawararki ko?"

Murmushin takaici na yi na ce." A a kai ne abokin shawarata Baba, magana muke yi akan Kamalu yana tambayata idan ya dawo daga makaranta a Ina zai zauna na ce masa can wurin kakarsu Gwaggo  mun yi magana da Hamusu zai dinga tafiya dashi kasuwa."

Ya gyada kansa yana dubana ya furta." Ashe kina bibiyar sha'anin yaron."
Cike da mamaki na ce sosai ma kuwa." Ya furta." Babu inda zai zauna sai nan tare da mu gabad'aya domin raba kan yaran zumuncinsu zai yi rauni, baya ga haka kuma, a can unguwar taku ya lalace ai, to me zai sanya kuma a sake mayar dashi, idan har kun yanke shawarar zamansa a can kano to  sai ku had'a da d'an'uwansa gabad'aya ku ajiyesu a waje daya."

Na yi shiru ina auna maganarsa. Gabad'aya kaina ya kulle na gaza fahimtar abinda yake nufi da wannan maganganun yanzu ina iya furta wata magana ya canza mini manufa, ni dashi duka ba mu da karfin iko kamar dangin Babansu. Hamusu kuma yana iyakacin bakin kokarinsa wajan ganin ya bashi girma kuma bashi da wata matsala, amma tunda sun nema kuma suna da

hakki akan yaran nan ya kamata a ce wannan karon na yi kawaici da alkunya na ba su daya na rike d'aya, amma ina ganin ba zan samu goyon bayansa ba, nema ma yake ya mayar da abin rigima da 'bangaranci.
Na share shi kawai ban ce masa komai ba domin ina danne zuciyata ne ba na son na biye masa na san idan muka fara ni dashi gabad'aya ba zata yi mana kyau ba."
Ya tashi zai fita na ce." A game da maganarka ta d'azu ina da ja kai."
Ya tsaya tare da juyowa yana kallona.
"Wace magana kenan."
"Dangane da amanar matarka da ka ce ka ba ni, ban kar'ba gaskiya domin ni ma nema nake yi ka ri'ke amanata don har yanzu ban san kaina ba."
Ya ce." Ai hakkinki ne a matsayinki na babba ki ri'ke mini amanar gida da duk wanda na kawo na ajiye shiyasa na gaya miki."
Na ce." Ban kar'ba ba gaskiya kuma zuciyata ba ta aminta da zamanta a samanka ba, idan adalci za ka yi kawai ka ce mata ta sauko kasa."
A nutse ya furta." Ba ki ji uzurinta ba ne, tana da ciwon kirji ta ce ko a wajan aiki a kasa take ba ta iya zurga-zurgar hawa sama."
D'auke kaina na yi ban ce masa komai ba. Ya ce." Idan kina ganin da damuwa to kema sai ki tattaro ki hawo saman ku tare bakidaya hakan zai fi."
"Ina buk'atar tsinka jinina, da zan hau ai da tun kafin ta zo gidan na hau."
Ya daga kafad'arsa ba tare da ya ce mini komai ba ya bud'e kofa ya fita.
Na ja jiki ahankali na kwanta saman gado ina matse jikina kawai na ji hawaye na fita daga idona.
Ajiyar zuciya na sauke tare da dan rintse ido yayin da damuwa ke sake sukar ilahirin jikina.
Daurewa kawai nake yi  ganinsa ya k'ara motsa mini bukatarsa da ta dame ni.
Haka na 'kàrasa yini na cikin damuwa da takura da daddare da kyar na fita falon shi ma don kada Hajja ta zargi wani abin ne, na same su kuwa gabad'aya har ita amaryar inda ta sheka ado da wani uban Les ta soka d'aurin dankwali wanda ya fito da k'arin gashin da ta yi. Kwaliyya ta yi sosai irin ta amare har dasu gashin ido ga sarka nan d'azu awarwaro da zubona a yatsun hannunta.
Ban damu ba domin abin da ya dame ni daban shiyasa adonta bai d'auke mini hankali ba, abinda dai ya so ya bata mini rai bai wuce ganinsa zaune a saitinta ba suna magana da juna.
Na yi 'kokari sosai wajan nuna ban san me suke yi ba, muka gaisa har shi din da yake dan satar kallona itama amaryar ta yi mini sannu da fitowa Hajja tana cewa" ai yanzu nake shirin aika Yusi ya kiraki."  Na ce." Wallahi ina yin sallar magriba bacci ya kwashe ni sai yanzu na farka.
Kafin tayi magana aka kira shi a waya maganarsa ta d'auki hankalinmu gabad'aya zance ne dai bai mutu ba domin iyalan wani mamacin ma sun sake yin magana a sahar nan ta fece book inda suma suke kalubalantarsa akan take hakkinsu da ya yi.
Gidan jaridar da duniya ta aminta da rahotanninsu sune suka kira shi domin neman k'arin bayani da kuma neman alfarma samun lokaci daga wajensa

don su tattauna ya kuma wanke kansa dangane da zargin da jama'a suke yi a kansa.....✍️
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram.Normal What'sapp group kuma #700*
*Hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*

*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*

*Cibiyace da tai fice wajen  gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar gurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*

*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*

*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*

*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*

*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*

*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*

*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*

*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*

*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*

*muna da mummuna da aiki*

*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*

*muna da kogin daɗi*

*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*

*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*

*7 days for chronic infections flusher*

*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*

*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*

*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*27*
Kafin ma ya kammala wayar Sukairaju ya shigo, ya d'an tsaya daga gefe bayan ya gaishe mu. Sai da ya bari ya gama tukkuna ya risina tare da mika masa wayar hannunsa.
Ya kar'ba kimanin minti biyar ya gama dubawa ya mika masa wayarsa a nutse ya ce." Kada ku damu in sha Allahu alheri ne, gobe za mu tattauna da gidan jarigar Amana daily trust zan wanke kaina bisa zargin da jama'a suke yi mini.,

Sukairaju ya sake risinawa yana fad'in." Ranka ya dad'e lamarin ne ya karad'a gari mussaman social media jama'a sai maganganu marasa dad'i suke yi akanka, dalilin da ya sanya hankalinmu ya tashi kenan"
Ya furta." No kada ku damu zai wuce an riski kalubale iri iri, an cimma nasara kuma, wannan ba komai ba ne, zan dai yi bincike akai sosai."

Hajja ta ce." Amma dai Alhaji Sammani bai kyautawa rayuwarsa ba wallahi, yanzu wanene ya san iya adadin mutanan da ya takewa hakki."
Ya ce." Sai Allah Hajja domin wad'anda suka rasu a 'karkashin ayyukana suna da yawa wallahi, kuma duk wanda na tabbatar da mutuwarsa zan fitar da hakkinsa na bayar, shi Sammanin shine ya zalince ni."
Sukairaju ya k'ara shigowa a karo na biyu da sauri ya nufo shi da waya, kafin ya k'arasa ya dakatar dashi yana cewa." Sukairaju na gaji da magana daya don Allah kada ka k'araso nan, na san inda matsalar take zan kuma yi maganinta."

Ya tsaya bai kàrasa ba kamar yadda aka umarce shi amma bai fita ba ya sake sunkuyar da kansa da ladabi ya ce." Sir lamarin ne ya sake yin tsamari ne wannan yana da kyau ka duba domin daga gida abin ya sake fitowa."
Shiru ya yi bai ce masa komai ba, sai hakan ya bashi damar isa wajensa ya mik'a masa wayar tare da nuna masa abinda yake zo ya gani.
Da sauri na ga ya d'ago kansa yana kallona da mamaki mai yawa a tare dashi.
Ban kawo komai ba balle na zargi abin ya shafe ni.

Ko da ya gama karantawa bai ce komai ba ya bashi umarnin fita. Numfashi ya fesar kafin ya yun'kura ya tashi ya nufi samansa ba tare da ya sake wata magana ba.
Gabad'aya hankalinmu ya tashi har mahaifiyartasa, ta ma manta wadda take dashi fadi take yi  Amina tashi ki bi shi maza domin yana buk'atar wani a kusa dashi.
Ni kaina sai bayan na tashi din ne naga kamar rashin dacewar hakan tunda ga amaryarsa a ganina ita ya kamata ta je kusa dashi.
Sai na dan tsaya da tafiya.
Ta sake fad'in." Maza ki je mana, kin san shekaru sun fara hawa kansa kada ya yanke jiki ya fad'i.
Gabana ya buga da karfin gaske dana tuna rashin lafiyar da yayi kwanaki fad'uwa ya yi har sai da aka d'auke shi bai san inda kansa yake ba.
Na nufi saman da sassarfa da fargabar abinda zai biyo baya.
yana zaune a gefan gado ya d'an tallafe ha'barsa da hannu kamar mai nazari na nufe shi yayin da tausayinsa yake tsirga mini, kusa dashi na zauna a nutse na ce." Baba kada tunani ya haddasa maka ciwo, kaifa babba ne, kuma kayi gwagwarmaya menene baka gani ba don Allah kada ka damu akan wannan abin, muna cikin tsananin bukatarka a yanzu."

Ya dube ni a nutse ya furta." Ke da yaranki Kuna buk'atar hakkin tsohon mijinki  Aminu Salihi wanda na take bayan rasuwarsa ko?"

Gabana ya wani buga da mugun karfi. Na zuba masa ido Ina kallo lebana yana rawa tsabar mamaki da tashin hankali.
Ya d'auki wayarsa dake saman dirowa ya farara labule. Minti uku ya miko mini, babu gardama na kar'ba wani pege ne da ban san me shi ba, akayi tagging dina wanda ya yi rubutun yana magana akan yadda Alhaji Tajo yake amfani da matasa domin tara dukiya har yana bada labarin Yaya Aminu da irin bautar da ya yi masa yana kuma jadaddawa a rubutunsa cewa da yawuna ya fito yake magana akan hakkina dana yarana da aka take.
Cikin wani irin yanayi na tsantsar damuwa da tashin hankali na shiga fece book din ina ta scrolling abinda yake ta trading kenan. 'Cewa jita jitar da ake ji dangane da Alhaji Tajo da ma'aikatansa gaskiya ne, domin kuwa matarsa wadda yake aure a yanzu tsohon mijinta Aminu Salihi kafin rasuwarsa ya yi aiki a karkashinsa wanda kowa shaida ne dangane da yadda ya bautata masa a wata majiyar ma ana cewa sanadiyar aikinsa ne ya kamu da lalura sa'i daya kuma ya kore shi daga aiki domin ya gane bashi da mamora karfinsa ya kare, bayan ya sallameshi daga aiki bai bashi komai ba, a haka Aminu Salihi ya yi ta jiyya har ya rasu da damuwar hakan. Rahoto ya tabbatar da cewa da yawun Aminu Salisu mai hula wannan 'yar kasuwar nan da ta yi shura wajan fashion designer a kafafan sadarwa da amincewarta wannan rahontan ya fita."
Gidajen jaridu da wanda suka kai da wanda basu kai ba sai posta hoto na da nasa suke yi. Wasu ma harda hoton yaya Aminu da Kamalu da Yusi.

Kuka ya k'wace mini da k'arfi na sanya hannu na toshe bakina Ina kallonsa hawaye na shatata.
Ya kar'bi wayarsa ya ajiye ya matsa daga kusa da ni, ya ja jikinsa ya jingina da allon gadonsa.
A hankali na matsa kusa dashi ina kuka na ce." Wallahi tallahi Baba ba da yawuna aka fitar da wannan maganar ba, asalima ban san me pege din ba idan ka lura sabon shafi ne ba a jima da bud'e shi ba, wata'kila an shirya mini hakane domin a 'bata ni a wurinka, ba zan ta'ba cin zarafinka a duniya ba Baba idan ban ya'da alherinka ba ai ba zan yad'a sharri a kanka ba, ka yarda da ni wallahi ba ni da masaniya abinda yake faruwa, babu hannuna."

Ya dube ni a yayin da na gama firgicewa domin hankalina ya kai ma'kura wajan tashi jin yadda lamarin yake nema ya sauya salo, hakika duk wanda ya shirya wannan lamarin ya yi mini farin sani. Na san dai kafin k'addarar aure ta ratsa tsakanina dashi a ko'ina na kan saki bakina na soki sha'aninsa na kushe shi, na nuna ba na daya daga cikin mabiyansa idan aka tambaye ni hujja ba na rufewa fad'a nake yi. Ban ta'ba tunanin hakan zai janyo mini gagarimar matsala ba tunda ban ta'ba zaton aure zai ratsa tsakaninmu.
Ganin yadda na kanainaiyeshi da ro'ko da magiya ya sanya ya sassauta fuskarsa ya gyara zamansa a tsanake ya dube ni yana ce wa." Me yasa tunda muka yi aure ba ki gaya mini cewa Aminu Salihi ne mahaifin Yusuf ba.
Hannu na sanya na goge hawayen da suke zuba na ce." Ban san ta yadda zan gaya maka ba wallahi, ni dai abinda nake so ka fahimta shine wallahi ba ni da hannu wajan wannan rubutun. Abinda na yi Imani dashi shine duk wanda ya shirya hakan yana da masaniya akan sha'anina."

Ya zuba mini ido kafin ya ce." To ke wa kike ganin zai hakan a cikin wad'anda ki ka sani ko kike tarayya dasu."
Na hada hannuna da nasa na rintse a na ce." Wallahi ba zance ba Baba, ka yarda da dani har cikin zuciyata babu mugun nufi a tsakaninmu."
Ya ce." Ai dama ni ma ban ce da mugun nufi ba, abinda dai ya fi damuna yadda ba ki sanar da ni cewa uban yaranki ya ta'ba aiki a k'arkashina ba, kin ga dole ne yanzu zuciyata ta d'ora zargi akan cewa da hannunki maganar nan ta fita, da kin sanar da ni tuntuni da Ina ga da duk haka ba ta faruwa."
A sanyaye na ce." Ban san ya za a yi na gaya maka ba, to na ce maka me? ya fa riga ya mutu shekara da shekaru kuma maganarsa a tsakaninmu zata iya haifar da wata matsalar maigirma."
Ya d'an jima yana kallona kafin ya ce." Ki gaya mini gaskiya shin bayan rasuwar Aminu Salihi Alhaji Sammani ya je ya yi muku ta'aziya ko bai je ba."
Girgiza kaina na yi a hankali na ce." Bai je ba."
Ya ce." Kin ga hakan yana nufin kudin dana fitar da sunan magada suna wajansa"

Shiru na yi ban ce komai ba, ni dai burina kada ya zarge akan abinda yake ta yawo a kafafan sadarwa.

Ya dan riko kafadata tare da sanya tafin hannunsa yana goge mini fuska ya ce." Daina kukan haka na aminta dake wata'kila ana bin ki ta karkashin kasa ne to sai aka samu wannan damar amma duk yadda akayi wanda ya fitar da maganar nan ya san ki ciki da waje, babu komai zai wuce in sha Allahu."
Yana maganar yana dan bubbuga bayana. Zuciyata ta dan yi sanyi amma har yanzu damuwar bata sake ni ba, domin yadda ake ta sukarsa ana yad'a sharri akan harkokinsa ya tsaya mini a raina.
Luwai na yi a jikinsa ina sauke ajiyar zuciya yayin da hannunsa yake dan dukan bayana a hankali a hankali d'akin ya yi shiru na tsayin mintina goma babu sautin komai sai na numfashinmu.... Daidai lokacin da nake yun'kurin zare jikina daga nasa ta turo d'akin ta shigo duk muka bita da kallo
Cikin 'yar fargaba na cire jikina daga nasa na d'an ja gefa, ta k'araso a nutse babu fara'a a tare da ita ta ce.'' Kin san dai ba haka ake yi ba ko? kada ki bud'e kofar fitina a tsakaninmu lamarin ba zai yi mana kyau ba wallahi, wace macece za ta yarda ayi mata wannan iskacin, aka ce ki zo domin ki kula dashi me yasa ba ki gayyace ni ba, a matsayin matarsa nake kuma amaryarsa me ya sa za ki 'kebe dashi kusan mintina talatin, kin san dai ko ke aka yi wa haka ba za ki ki dadi ba."
Shiru na yi ban ce mata komai ba, domin duk maganganunta akan hanya suke tana da gaskiya kuma ko ni ce ba zan yarda ba gaskiya dalilin ma da ya sanya kenan na ja bakina na yi mata shiru tana ta furzar da takaicinta. Jin tana sanyo Hajja a ciki ya sanya ya ce." Ba za ki yi mana shiru ba ko? ke wai me yasa ba kya aiki da iliminki ne, me ki ka shigo ki ka ina yi da ita da kike so ki zage ni."

Sai ta rushe da kuka tana cewa." Ni ba da kai nake ba, ai ta san ba ta kyauta mini ba shiyasa ta yi shiru bata da gaskiya, kai kuma kana biye mata, har kana so ka kare ta."
Yunkurawa na yi na tashi domin fita daga d'akin ta bi ni da harara tana jan tsaki ban kulata ba na kama hanya na fice zuciyata a cunkushe.

Ban iya rintsawa ba a daran ranar raba dare na yi ina duba comments din mutane dangane da abinda yake faruwa wasu sai zagina suke yi suna fad'in dama ba ni da kunya sannan kuma butulu ci na yi masa ban kuma san alheri ba. Tsirarun wad'anda suke goyon bayansa sune suke fad'in wannan maganganun. Amma dai masu zaginsa sun fi rinjaye.
A daran dai na shiga fege dina na fece book din a karo na biyu zan sake yin rubutu akansa wannan karon rubutuna yana d'auke da sa'kon godiya da yabawa, jinjinawa da sadaukarwa a gare shi, na kuma fito na gayawa duniya cewa babu yawuna dangane da rubutun da yake ta yawo a kafar sadarwa asalima ban san me pege din ba, na rufe da yi masa kyawawan addu'oi tare da samun cigaba da d'aukaka da kuma gamawa da duniya lafiya.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce

wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*

*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*28*
Washe gari da safe ban fita da wuri ba sai wajan takwas da rabi. Hajja kawai na samu a falo ita kad'ai.
A nutse na kàrasa wajan da take na tsuguna na gaisheta kamar koyaushe ta amsa tana d'an bina da kallo, matar tana da saurin fahimtar mutum ko yaya ta ga can ji a tare dani sai ta nemi ba'a si, a nutse ta ce." Zo zauna kusa da ni, na ji me yake faruwa Amina wannan kumburin na Idonki ba na lafiya ba ne."
Na zauna gefanta ina dan murmushi wanda sam babu nishadi a cikinkisa.
Ta ce." Menene yake faruwa?

Cikin rauni da damuwa na ce." Wallahi Hajja wani abu ne ya faru wanda bai yi mini dadi ba ko kad'an, wani rubutu ne ya fita da sunana a ciki wai ina neman hakkin yarana a hannun maigidan nan, mai rubutun kuma yana jadaddawa duniya cewa da yawuna ya fito yake sanarwa mutane."
Ta ce." Assha to shine ai me kuma? Idan ma kin fito kin yi magana ai ba lefi ba ne, abinda dai nake so na fahimta shine dama Babansu Yusi din ya yi aiki a karkashin Tajo ko kuwa?"

Hajiya lallai idan kina karanta littafin nan kuma ba ki biya ni hakkina ba, to Ina me tunasar dake girman hakkin mutun da wahalarsa. Ki biya ni gumina kafin ki karanta mini littafi.

Na goge hawayen da ya dan zubo mini na ce." E, ya yi aiki dashi kafin rasuwarsa."
Sai ta girgiza kanta cikin alhini ta ce." Allah Ya gafarta masa, ki samu nutsuwa kuma ki daina damuwa da hakan in sha Allah babu abinda zai faru."
Na ce." Na gode Hajja Allah ya kara girma." Ta dafa kafadata tana cewa." Ina ganin umarar nan tare zamuje ki d'an samu nutsuwa ki kuma yi addu'oi, Allah ya shiga tsakanin nagari da mugu."
Na kalleta hawayen da nake ta dannewa suka fara zuba, na rasa wane irin so da k'auna baiwar Allah nan take yi mini, tana gudun b'acin raina sosai, tana kuma so koyaushe ta gan ni, cikin farinciki da walwala. Na ce." To shikkenan Hajja sai mu tafi taren in sha Allahu."
Hauwa ce take saukowa daga bene tana sanye da kanun kaya amma ta dora after dressing akai ta yi kwalliya sosai a fuskarta kuma ta yi kyau daidai gwargwado.
Ta iso wajan da muke zaune ni da Hajja ta zauna saman kujera tana fad'in." Hajja Ina kwana an tashi lafiya?"
Ta amsa da "Lafiya lau tana dan dubanta."
Ta d'an kalleni kafin ta ce." Ina kwana." Na amsa babu yabo babu fallasa."
Hajja ta ce." Tajo bai tashi ba ne?"
Babu kunya balle tsoron Allah ta ce." Bai tashi ba jiya bai kwanta da wuri ba."
Hajja ta yi shiru tare da kawar da kanta gefe. Ni kam maganar ta dan dake ni sai nake ganin kamar da gayya ta fad'eta."
Tashi na yi na nufi wajan cin abinci ina fadin." Hajja kin karya ne?"
Sai ta ce." Kin manta yau litinin ina Azimi."
Na ce." Wallahi na manta, Ina gyara kujerun wajan na dubeta." Hauwa ki zo mu karya."
Ta d'an yatsune baki tana cewa." Ina ga sai an jima ba na karyawa da wuri."
"Okey kawai na ce na gyara kujera na zauna a nutse na dan d'ibi abinda zan iya ci na hada tea na fara sha domin ya d'umama mini cikina.

Saukowarsa ta d'auki hankalinmu gabad'aya duk muka zuba masa ido yanayinsa kawai nake kallo kamar ba shi wanda ya shiga damuwa mai tsanani jiya ba. Ban d'auka zai wayi gari da karsashi irin haka ba. Kwalliya ma ya sheka sosai cikin wani irin yadi irin na manya babbar riga da yar ciki

da uban aiki a gaban rigar.  Tun kafin ya k'araso wajan da muke kuwa kamshinsa ya karad'e mu.
Ya risina yana gaishe da Hajja ta amsa tana cewa." Ban jima da tambayar Hauwa ba ta ce wa ai baka tashi ba."
Yana dan gyara agogon hannunsa ya furta." Eh yau na dan so na makara ne wallahi, ina da baki a waje zan fita wurinsu yanzu za mu interview."
Ta ce." To babu damuwa." Ya nufi hanyar fita bai dube ni ba. Abin ya sosa mini rai 'kwarai da gaske amma ban kawo komai ba illa iyaka azijanci irin na d'an adam, domin yadda ya sauko a gurguje wata'kila bakin masu muhimmanci ne. Ni kadai nake wannan hasashen a cikin raina. Ko minti biyar bai yi da fita ba Hauwa ta tashi ta haye sama ta bar mu a wajan ni da Hajja.

'Danjaridar ya ce.
"Da farko Allah ya taimake ka muna so mu ji daga bakinka dangane da jita jitar da take yawo a gari mussaman a kafafan sadarwa, inda kowa yake tofa albarkacin  da yake bakinsa dangane da mutuwar wani ma'aikacinka da iyalinsa suka fito suna kuka akan cewa ka yi amfani da lafiya da kuruciyarsa a lokacin da yake raye domin neman dukiya karshe ajalinsa ya sauka a karkashin aikinka, ba ka je ka yi wa iyaye da iyalinsa ta'aziya ba, sannan kuma babu ihsani a tsakani, mutane da dama suna zarginka akan son zuciya da ko'karin tara dukiya domin ka gina kanka."
'Dan jaridar ya nisa kafin ya cigaba da cewa." To ana cikin wannan turka-turka a gari da sauran kafafan sadawarsa sai ga wata majiya mai toshe ta yi sanarwa kan cewa Matarka ta yanzu wadda a can baya ta ta'ba auran wani Aminu Salihi wanda ya kowa ya shaida cewa ya wahalta maka k'warai da gaske dalilin lalurarsa yana da ala'ka da abinda ya shafeka, ya kwanta jiyya ba ka duba shi ba, ba kuma ka aika wakili ba, ya fadi ya mutu ba ka je ta'aziya ba sannan ba ka yi ihsani ga iyalinsa ba. Wannan dalilin ya sanya itama matarka ta yanzu ta fito take nemawa yaranta hakkinsu a wurinka, Allah Ya k'ara lafiya ko za a yi mana karin bayani dangane da zargin da jama'a da masu hakki suke yi maka.

A tsanake ya yi sallama da mika godiya ga Allah da salatin annabi sannan ya fara da ce wa."
Ni dai Alhaji Tajudden Ibrahimu 'Danbatta a iya sanina da hasashena babu wani wanda yake karkashina da hakkinshi yake a wuyana. Tabbas wannan ka'idata ne kuma tsarina ne ba na d'aukar tsaffi aiki, matasa majiya karfi nake d'auka. A cikin matasan ma muddin na fahimcin gazawar wani nakan sallameshi na maye gurbinsa da wanda na tabbatar da cewa za mu taimaki juna.
Ma'aikatu nake dasu ba gwamnati ba ce ni. Babu yarjejiyar fansho da garatuti a form dina. Duk wani ma'aikici na ya san da wannan ya kuma amince da hakan.  Ra'ayina ne yin alheri ga duk wanda na sallama saboda wani dalili, ra'ayina ne yin alheri  da ihsani ga iyalan wanda ya rasu a karkashina, amma abinda nake so mutane su fahimta anan shine ba dole ba ne, ba kuma tilas ba ne in d'auki kudi na bawa wanda ya mutu ko wanda na

sallama daga aiki kamar dai yadda na fad'a da farko ni ba gwamnati ba ne. Kuma maganar da mutane suke yi akan ba na zuwa ta'aziya ko dubiya wannan sharri ne aka yi mini. A duk lokacin da wani lamari ya faru muddin ina gari na kan yi kokari na je, idan kuwa wani uzuri ya rike ni na kan tura Alhaji Sammani da 'yan tawagarsa wad'anda duk suke a k'arkashin ikona kuma da alheri mai yawa. A lokacin da Aminu Salihi ya rasu ba na gari, kuma Allah ne shedata na tura a je a yi musu ta'aziyya tare da miliyar biyar domin a bawa magada, wannan shine abinda na yi. Ina so na gayawa duniya cewa' duk wannan maganganun da suke ta yawo akaina ba ni da hakki ila iyaka wanda na  d'auki Amana na d'amka masa shi ya zambace ni. Babu wanda bai san yadda nake da Alhaji Sammani ba. Yau na fito na gayawa duniya cewa Sammani ne ya haddasa wannan lamari kuma ban fadi hakan domin na 'bata shi don na wanke kaina ba. A duniya kana iya zama da mutum da zuciya daya har ka dinga ya'kini a zuciyarka ba zai ci amanarka ba amma daga baya a samu matsala. Abinda ya faru kenan a tsakanina da Alhaji Sammani sai gashi lokaci kan'kani yana nema ya kai ni 'kasa, to saboda haka masu zargina da zagina  ku bari domin ba ku da hujjar yin 'batanci a gare ni, sai ma dorawa kanku zunubi mai girma da kuke yi."

Cikin sanin makamar aiki d'anjaridar ya ce." To Allah Ya taimake ka za mu su mu ji karin bayani daga bakinka dangane da maganar da fita jiya da daddare wanda ake ta jita-jitar cewa da yawun Uwargidanka maganar ta fita, masu bibiyar sha'anin za su so su ji wani karin haske daga bakinka"
Dariya ya yi kafin ya ce." Babu yawun matata dangane da maganar jiya. Ni asalima ban san cewa tsohon mijinta ya yi aiki da ni ba sai da maganar nan ta fita, idan ma da yawunta a maganar ban ga aibu ba domin ta fito ne a matsayinta na uwa tana nemawa yaranta hakkinsu kamar dai yadda sauran mutane suke fitowa. Da ita da sauran iyayen marayun da suka yi magana na yi alkawarin bawa kowaccensu miliyan biyar biyar domin dogo da kai, kuma su kula da yaransu. Wannan na yi ne saboda Allah, sannan kuma har yau hanya a bud'e take ga duk wanda yake da k'orafi akaina zai iya tunkarata kaitsaye idan kuma hakan zai yi masa wahala zai iya isar da sakonsa ta kafafan sadawarsa domin korafinsa ya isa gare ni, a shirye nake da bawa matasa gudumuwa muddin sun bu'kaci hakan daga wurina."

Wannan maganar tasa ta k'arshe ita ta karya karsashin d'anjaridar duk k'wakwarsa sai ya rasa abinda zai fad'a domin kuwa an riga an dabaibayeshi da halin girma da dattako.

To abinda ya dinga tashe kenan a kafafan sadarwa. Wasu na fad'in hirar a rubuce ya yin da wasu ke d'ora bidiyon hirar a shafikansu ana ta zuba sharhi da cacar baki da bawa hammata iska idan aka samu b'angaranci daga mabiya dake comment section.
An nufe shi da sharri sai kuma Allah Ya juyar da lamarin mabiyansa suka kara ninkuwa sakamakon hirar da aka yi dashi kuma yawancinsu duk matasa ne majiya karfi wanda suka rasa abin yi.

Ni kaina na ji dad'i sosai dana saurari hirar mussaman wurin da ya wanke ni daga zargin da jama'a suke yi mini, duk k'wakwar d'anjaridar bai yarda ya soke ni ya soki iyayena ba, yana ta ko'karin kare mini mutunci amma hakan bai hana shi azabtar da ni ta karkashin kasa ba, gigin sabon aure ne ko tasirin asiri na kasa gane wanda yake dawainiya dashi sai sha mini kamshi yake yi
abinda na lura dashi shine tun ranar da Hauwa ta kwana a dakinsa wasu daga cikin al'amuransa suka canza. Mussaman daga 'bangarena. Bai iya tsayawa ya 'bata lokaci mu yi magana ba. Yau kwana uku kenan tare suke kwana na riga na san hakan dole zai faru tunda kwanaki bakwai musulunci ya tanadar mata shiyasa kwanansu bai daga mini hankali ba
Yadda dai ya canza a lokaci kan'kani shine abinda ya fi damuna tun washe garin ranar da suka kwana lamarin ya sauya salo. Zuciyata ta dinga yi mini sa'ke-sake akanta domin dai Ina ganin akwai hanyoyin da tabi wajan janye masa hankali ko asiri ko amfani da maganin mata. Sau daya dana hau samansa da zummar gaisuwa na fuskanci fuskar gizako ban 'kara marmarin sha'awa hawa ba, domin ba na so ko yaya ne ya yi mini abinda zai sanya ta samu kofar yi mini kallon banza.....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp Group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN🖊*


TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky


*TALLAH!*

*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*

*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*30*
Ta juya da kuzarinta tana fad'in." Bari na gayawa maigidan cewar b... Bata kàrasa ba na katse ta hanyar fad'in." Saki na yi?''
Sai ta juyo tana kallona. Na dubi tsabar idonta na ce." Ban sanya ki ba, don haka cire kanki daga wannan sabgar ki kalleni da kyau ba sakarai ba ce, balle ki ce za ki yi mini ta 'yan duniya kallonki kawai nake yi Hauwa."
Murmushi ta yi sai kuma ta d'an ta'be bakinta ta ce. " Menene abin fusata ranki ya dad'e, ni menene nawa a ciki, ba ni na kar zomon ba, zaman tare ne fa ya sanya na shigo dakinki, hakki ne na musulunci, ni kuma ba zan yi gaba dake ba domin ba dabi'ata ba ce hakan, amma ki yi hakuri idan abinda na yi miki ya 'bata miki rai."
Ban tanka mata ba har ta gama maganarta ta fita na ja tsaki mai karfi tare da kawar da kaina gefe.
Yusi da kansa yake sunkuye tunda muka soma maganar ya dago cikin yanayi na sanyi jiki da rashin jin dadin abinda ya faru ya ce." Mama to kin ce kada ta baki magani, kuma kin ce kada ta gayawa Baba yanzu ya za a yi to."
Shiru na yi ban ce masa komai ba domin har yanzu raina a b'ace yake dangane da rainin hankalin da Hauwa take ko'karin yi mini.
Wato ta fahimci zaman doya da manjar da muke yi shine da 'kumaji da gwarin guiwarta take taka 'kasa da ko'karin mayar da ni wawiya.
Yusi ya dame ni da magana na buga masa tsawa raina a b'ace na ce." Idan ba ka yi mini shiru ba wallahi sai ranka ya 'baci yanzu nan, idan na mutu ai lokacina ne ya cika, ba wanda zai jira duniyar kowa sai ya mutu.
Sai ya fashe da kuka tare da sanya kansa a tsakiyar gwiwarsa. Na janye idona daga gare shi na cigaba da tunanin hanyar da zan bi wajan ganin na dafa mutumin nan cikin ruwan sanyi domin zuciyata na ga alama ba zata iya juriyar nan da anti Yagana take ta nanata mini ba, a yanzu da ni bana tsoro ko fargabar a lissafa mini auran ai ba ni kadai ba ce.

Kada ki karanta littafin nan ba tare da kin biya mai hakki hakkinta ba. Mu kula sosai da hakkin wani akan mu. Allah Ya sa mu dace Amin.

Wajan tara da kwata na dare ya shigo dakin. hankalinsa yana kan Yusi dake can kan dadduma a kwance ya ci kuka ya koshi, na yi na yi dashi ya fita ya ci abinci ya'ki, biscuits din da nake ajiyewa a d'akin ya ci da lemo kawai ya ha'kura, ni kuwa dama damuwar da nake ciki bata barni sha'awar komai ba.
Kallo d'aya na yi masa na janye idona daga kansa Ina dan hade jikina sakamakon jin yanayina na nema ya sauya.
Ni na san wannan rikicin da nake ji baya rasa nasa da buk'ata irin ta gangar jiki. Tun kafin auransa da Hauwa bukata take damuna tun ranar da na banki magunguñ nan, ranar d'aurin auransa kenan, har muke je saudiya muka dawo abin na damuna kawai ina dannewa ne, abinda jiki ya riga ya saba dole idan ya buk'ata bai samu ba ya shiga wani yanayi. Ba zan ta'ba nemansa ba abinda na kudire kenan a raina.
Ya je ya daga shi a rikice yana fad'in." Kai aboki menene haka? ba ka da lafiya ne?" yana maganar yana tattaba wuyana.
Yaron ya share hawayen dake zubo masa. Ai sai ya kara rikicewa ya dago shi sosai yana kallona ya furta." Bashi da lafiya ne?"
Share shi na yi ban bashi amsa ba.
Da gaya haka sai ya sake mayar da hankalinsa kan yaron yana tambayarsa. Da 'kyar muryarsa can kasa ya ce." Mama ce bata da lafiya shine take cewa mutuwa za ta yi?"
Ya dago da sauri yana kallona, ban dube shi ba ina dai kallon duk wani motsinsa ta gefan Idona.
Sai ya tashi yaron tsaye ya riko hannunsa suka nufo wajena, sai a lokacin na dubesu ina daga kwance ban motsa ba ya zauna kusa da ni shi kuma Yusi ya tsaya saitin kaina tare da dora hannunsa a saman goshina.
"Me yake damunki?" Yafada da 'yar kulawa.
A takaice na ce." Me ka ga ni?"
Ya zuba mini ido da yanayi na jin haushin amsar dana bashi. Ya girgiza kansa kafin ya dubi Yusi ya ce." Ka je wurin Antinka tana da abu mai dadi ka ce in ji ni ta baka."
Ya amsa da "To." Ya kama hanya ya fita. Ya juyo gare ni sosai yana cewa." Ki gaya mini abinda yake damunki domin ba ni so Allah Ya kama ni da hakkinki, ni dai nawa hakkin da ki ka take kullum ina gayawa Allah ya bi mini."
Jin abinda ya ce sai na tashi zaune sosai na dube tare da cewa." Hakki kuma na nawa ka take mini, ba ni da buk'atar kasan abinda nake ciki a halin yanzu domin abinda ya shafe ni."
Ya gyada kansa da fad'in." Okey to bari ba kira Antinki don na lura ita kadai zata gaya miki ki ji, yadda kike tsoranta ba kya tsoron mahaifin.....Kafin ya k'arasa na buga katifar gadon da k'arfin gaske na bude muryarta sosai na ce." Kada ka kuskura wallahi, na gaya maka duk abinda za mu yi ni da kai sunan mahaifina ya daina fitowa daga bakinka, idan babba ya zubar da girmansa sai karami ya hau ya taka, ba fa zan lamunta ba wallahi, ban raina naka iyaye ba ban ga dalilin da zai sanya ka raina nawa ba."
A tsanake ya ce." Rashin kunya ba inda zata kai ki, burunki na sake ki kije ki cigaba da harkokin tallata sura a social media ni kuma ban zan sake ki ba

wallahi, domin duk inda aka je aka dawo za a ce Tajo ya ta'ba auranta, kin ga kenan yadda ki ka 'bata sunanki ni ma kin 'bata mini nawa."

Rashin abin fad'a ya sanya na ja masa wani irin tsaki mai tsayi. Na koma na kwanta yayin da wani malolon abu ya dabaibaye mini wuya. Ya biyo ni gadon ban ankara ba ya sanya yatsunsa akan le'bena ya murde da k'arfin gaske yana fad'in. " Wallahi hukuntaki  zan yi kuma na kwana lafiya, mace tana girma amma tana cin kasa. Kuka ne ya kufce mini da k'arfi kamar zararriya na tunkud'eshi kawai sai na rufe shi da duka da hannayena duka biyun kuka nake yi haik'an takaicinsa ne zai halaka ni.
Ya daddaneni sai kuma ya tashi da sauri ya je ya rufe kofar d'akin ya dawo. Hasken ya kashe d'akin ya yi duhu.
Ganin haka sai na dawo hayyacina na tafi tunanin abinda zai yi. A dan hasashen da na yi na hangi yana cire rigarsa. Da sauri na dira daga gadon na je na kunna haske d'akin na ganshi gabad'aya ya cire kayan jikinsa haihuwar uwarsa.
Gabana na fad'uwa na ce. " Ka zo ka fita mini daga d'akina.
Ya nufo ni jale jale yana fad'in." Ni da gidana da d'akina da kuma matata a ce na fita lallai ma."
Na juya zan bud'e kofa na ga babu mukulli. Lokacin ya isko inda nake na yi saurin dauke kaina saboda kallon yanayin da yake ciki. Lallai namiji bashi da kunya zir haihuwar uwarshi fa.
Kirjinsa ya had'a da nawa ya manne a jikin bango.
Ya zira hannu da k'arfi ya rike 'kunguna. Ha'bata ta sauka a kafad'arsa na ji yana cewa." Ki kore ni mana idan kin isa, gidana ne fa."
Cikin kuka na ce." To me za ka yi mini. Bai tanka mini ba illa sansanar jikina da yake yi kamar karen da ya jima yana farautar nama.
 Zubewa muka yi a bakin kofar dalili ni kaina duk dauriyar da nake yi abun da yake yi mini ya fara sa'bata. Faduwarmu rigijif ya yi daidai da lokacin da Yusi ya zo yana buga kofar. Gabana na fad'uwa na ture shi na tashi da sauri na bar shi a wajan.
Ya ta so ya nufo ni a ki'dime Yusi na cigaba da buga kofar d'akin.
Na dube shi na ga duk ya wani rikice kuma ba shi da alamar bud'ewa sai ma ya rikito kan gadon yana janyo ni, na matsa da saurin gaske ba wai bukatarsa ne ba na yi ba, halin takaicin da nake ciki ne ya sanya nake ganin k'yashin bashi kaina.
Jin shiru an daina buga kofar ya tabbatar mini da cewa yaron ya matsa daga wajan.
Kokawa katitir muka dinga yi ni da shi, tun Ina ji da kuzari da karsashin yin kokawar har gab'obina suka sage saboda ya fi ni k'arfi kuma matsa yake yi mini ta rashin imani a haka duk ya ta'be mini kirji suka dinga zafi, sosai na galabaita na zauna kusurawar gado ina kuka shi kuma kamar tsohon maye ya haka ya zame mini, duk abin nan babu suttura ajikinsa sosai hakan ya dinga ba ni mamaki wato shi kunya gaba ya bata ba baya ba.

Na juyar da kaina gefe don har na gaji da kallonsa a haka ya janyo k'afata cikin sigar so lallai sai mun cigaba da yi yana fad'in." Ta ji tsoro a bata ruwan mad'aci."
Na yi shiru ban tanka masa ba, gwiwar hannuna ce kawai take ciwo kuma shine ya kwalmad'e mini ita.
Ya tale mini k'afafuna ya tusa kansa a tsakiyata. Tsigar jikina ta yi tsananin tashi. Na sanya hannu da k'arfi na cire kansa yana sake mayarwa ina cirewa tare da ran'kwashinsa da gwiwar yatsuna.
Cigaba ya yi da tura kanshi tsakiyar cinyoyina yana sa hannu Yana janyo kafata. Hankalina ya tashi ya riga ya san ta hanyar nan ne kadai zai iya cin galaba akaina. Idan ma na yi yun'kuri domin fita daga tsakiyarsa kamar taimaka masa na ke yi, dole na ha'kura na kyaleshi a lokacin ma jikina gabad'aya ya gama rikicewa tsantsar fitinata ta tashi, na lumshe idona numfashina na fita a hankali a hankali. Ina jin ya lura da hakan yana tunkuda kirjina na yi flat a gadon ya bini ya danne shikkenan kuma ban sake tuna komai ba. Abinda dai yatsa mini a k'wa'kwalwata sambatunsa na yau ya fi na koyaushe kuka kuwa sai kace sabon 'dan yaye yana yi, yana kuka kamar wanda aka aikowa da mutuwar iyayensa abin na yau ya shaddade kwarai da aniya ni kaina sai da na koka ganin yana nema ya kwana a kaina, da kyar ya ha'kura, gefen asubahi ya ce sai ya kuma yi. Na rushe da kuka dashi domin duk kwadayina akan abin ji na yi ba zan iya jura ba, saboda jiya nan ya gurje ni kamar sabuwar amarya, kawai dama ya tanadi wannan ranar nan ne don ya fanshe kwanakin da ya yi bai kwanta da ni ba. Kukana bai hana shi yi ba duk da bai samu hadin kai dari bisa dari ba, ya yi nishadinsa sosai, ni kam ya riga ya goge mini hadda jiya nan shiyasa ban fitar da komai ba.
Ana kiran asubahi ya rabu da ni.
Sai da ya yi wanka tukkuna ya fita daga d'akin.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#

VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*

*muna da kogin daɗi*
 *Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
 *muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*31*
Mamaki mai yawa ya dabaibayeni. Shin auran da ya yi ne ya kara masa fitina, ko kuma kawai dama ya shirya yi mini haka. Yanayinsa gabad'aya ya canza har karfi da kuzari ba kamar farkon auranmu.

Bai dawo mini d'aki ba tun bayan da ya fita da asubahi.
Na san dama da wahala ya dawo din dalilin da ya sanya ni kenan na hau saman wanda na fi wata rabona da hawa.
A bakin baranda na ji maganganunsu ita da shi kamar dai kowanne a fusace!
Ganin hakan ya sanya na juya zan sauka daidai lokacin ta bude d'akin ta fito tana goge fuskarta. Kallon juna muka yi, ba ta ce mini komai ba, ta bude dakinta ta shiga wanda yake kusa da nasa.
Cikin zuciyata na ce in dai namiji ba ki fara kuka ba Hajiya balle wannan mijin naki da rikicin tsufa ya fara ta'ba shi.
Ganin ta fito daga d'akin ya sanya na shiga. Yana zaune saman sofa da Laptop a gabansa. Ya dago ya kalleni ba tare da ya ce komai ba ya mayar da kansa yana cigaba da abinda yake yi Hakan da ya yi ya sanya na kama kaina. Na zauna ina fuskantarsa babu sukuni na ce." Ina kwana."
Ya amsa amma bai dago ba."
Na d'an zuba masa ido Ina nazarinsa wato kamar ba shi ne mutumin nan na jiya da daddare ba, sai wani hade rai yake yi.
Na gyada ina dan jin zafi abinda yake yi mini a cikin raina. Gabad'aya yanzu ya gama sare mini, kuma dama tun farkon auranmu ban manta ba ya ta'ba gaya mini Allah ya ba ni ha'kurin zama da halinsa. Ashe ya san yana da wahalar sha'ani.

Wata'kila dama yana jira mahaifiyarsa ta tafi sai abin ya k'ara tsamari tunda tun tana nan yake d'an yi, yanzu kuwa babu wadda zata gaya masa ya ji. Itama Hauwan wanene ya san abinda ya guma mata.
Na daure zuciyata na ce." Dama zan gaya maka ne jiya anti Yagana take gaya mini ana biki a can garinsu mamanmu maiduguri shine aka ce a gaya mini, to ina so zan shirya gobe ko jini sai na wuce."
Ya yi shiru bai ce mini komai ba, kamar ma bai ji abinda na gaya masa ba.
A da kufule na ce." Ka ji."
Bai dube ni ba ya furta." Ban bari ba."
Sai na ji wani 'kullutun abu ya tokare mini a wuya, duk irin suburbudar da ya yi mini jiya da abinda zai saka mini kenan, ai tsayin shekara da wani abu ban ta'ba tambayarsa zuwa wani wuri ba, ban yi tsammanin zai hana ni ba.
Zuciyata na yi mini zafi na ce." Dada ce fa ta ce a sanar mini, 'yan uwa duk za a had'u kowa zai je, to ni me yasa zaka hana ni, tun fa da na zo garin nan shekara har da doriya ban je wani wajan ba."
"Ni dai na ce ban bari ba." Ya fad'a hankalinsa a kwance.
Kawai sai na ji hawaye sun fara gudana a kumatuna. Ina jin dai d'an tahalikin nan ciwo yake so ya haddasa mini.
Ya dago kai yana kallona lokacin da kukana ya yi karfi.
Sai ya mayar da kansa ya rufe laptop ya rufe ya dan gyara zamansa yana dubana amma bai ce komai ba.
Naja hanci a shake na ce." Wannan zalincin ya yi yawa, kwata-kwata ka hana zuciyata nutsuwa kullum sai ka gumama mini b'akinciki, ban san me na yi maka a rayuwa ba a rayuwa."
Ya ce." Me na yi na zalinci, ba yunwa ba ishirwa haka zalika ba tauye hakki a shimfida, don kawai na hana zuwa unguwa shine zalinci."

Na ce." Zalinci ne mana, kana fita ka yi walwala ka hadu da 'yan uwanka ku gaisa, ni ma na gaya maka Ina so na ga dangina domin Ina kewarsu ina so kuma zuciyata ta samu sasaauci."

"Ko da ke, ko babu ke, za su yi bikinsu, ba ni so iyalina su yi nisa da dai kusa ne sai na barki amma gaskiya maiduguri ya yi nisa, kuma kin ga sai kin yi kwanaki kafin ki ce zaki dawo."
Jin ya fadi haka ya sanya na ce." Ai kai zaka fad'i kwanakin da zan yi."
Ya yi shiru yana lumshe ido kamar me shirin bacci.
Na dawo kusa dashi na zauna na ri'ke hannunsa a hankali na ce." Ka ji my love."
Ya bude idonsa da suka dan canza yana kallona ya ce ." Yaushe rabon da na ji wannan sunan abakinki, yanzu ai kina bukatar zuwa biki ko?"
Shiru na yi ban ce komai ba.
Ya girgiza kansa tare da sake rufe idonsa. Jikinsa na sake matsawa sosai a hankali na ce." Ka ji sweet love." Bai tare da ya bud'e idonsa ba ya ce." Matsa kada ki sanya na yi abinda ban yi niyya ba."
Ban matsa ba, sai ma hannuna dana sa Ina d'an jan gemunsa a hankali.
Ya bude Ido muka tsirawa juna ido.

Hauwa ta turo kofar d'akin ta shigo hannunta ri'ke da wani kwando cike da kayan abinci.
Janye idonta ta yi ta wuce can wajan da yake zama domin cin abinci ta fara shirya wurin.
A hankali na dan matsa daga kusa dashi ina fad'in." Ka amince ko?"'
"Zan yi shawara tukkun zuwa yamma zan gaya miki abinda na yanke."
Don kada ya tsinka ni a gabanta ya sa na tashi daga kusa dashi ba tare da na ce komai ba na kama hanya fita. Na ji ta ce." Amina tsaya kawai a yi ta ta kare, ba zan bari a ginu a haka ba domin dukkaninmu musulmai ne, ba maguzawa ba, idan shi mijinki yana jin tsoronki, ni gaskiya ba a haifi wata mace da zan ji tsoro ba, kuma ba zan yarda na yi zaman boranci ba, ba kuma zan yarda a tauye mini hakki ba."
Na ce." Akan me kike wannan zantukan."
Da mamaki da takaici ta ce.'' Au tambayata ki ke yi akan me nake yin magana."
Na ce." 'Kwarai kuwa."
Yana zaune yana jin mu bai ce komai ba.

Ta ce." Jiya girkin waye?"
Na ce." Oho!"
Ta zo iya wuya kawai sai ji na yi ta lallayo ashar ta jefo mini tana huci." Ni za ki mayar sakarai, kina abu kamar mai tabin kwakwalwa, na rantse miki da Allah ba za mu wanye lafiya dake ba, tunda ni ban shiga huriminki ba, ba zai yiwu ranar girkina ki dinga yi mini kutse ba."
Na dube shi shima yana cike da mamakin zagin da ta yi don sai hararta yake.
Na ce." Ka ji tana zagina ko?"
Ya ce." Je ki kawai, ki kyale ni da ita."
Ta kara fusata tana cewa." A dake ni a hana ni kuka, kuma a ce ba zan yi magana ba, sai ta fashe da kuka mai karfi
Ya ce." Idan zagi ne ni zaki ga domin ni na kwana da Amina a ranar girkinki, amma ita bata da lefi, Hauwa wannan ya zama na farko ya kuma zama na karshe kada ki kuskura na kara jin zagi a gidana, kin nuna mini rashin tarbiya da kuma rashin aiki da ilimi.
Ni ba namijin da mace take d'agawa hankali ba ne, ni na yi miki ba daidai ba, a wurina zaki nemi hakkinki, ita Amina ai bata da lefi.
Ta sake fusata tana cewa." Haka zaka ce ko? Ni me yasa ba ka nemana a ranar girkinta duk da bata zuwa dakinka ai baka taba zuwar mini da bukata ba."
Ya ce." Ai shiyasa na ce miki a wajena za ki nemi hakkinki, domin itama dole na yi mata."
Ina tsaye ina jinsu duk abinda ta fad'a a kaina sai ya tare maganar yaki bari sunana ya fito. Cikin raina na ce idan don na ji dad'i ne ban ji ba, domin kuwa wataran ni ma zai iya kware mini baya a gabanta, na bude d'akin ba fita na barsu suna ta turzawa, amma na yi mamakin sosai, domin ni a tunanina tunda ba na zuwa dakinsa ranar girkina ita da shi suna kwanciyar aure, ashe

zargin hakan kawai nake, ashe shine dalilin da ya sanya jiya ya famshe kwanakinsa.

Yini na yi cikin zullumi da tunanin zai barni ko ba zai barni ba.
Har na yi shirin kwanciya sai gashi ya shigo shi ma da shirin kwanciyar na zuba masa ido har ya k'araso ya zauna a gefana, yadda nake kallonsa shima haka yake kallona.
Na daure na ce." Da ka sani ka ce na fito falo sai mu yi magana, kada ta zargi wani abu."
Ya ce." Ina jin tsoronta kenan?"
Girgiza kaina na yi a hankali na ce." Ba haka nake nufi ba, kai zaka nemi zaman lafiya a gidanka."
"Kada ku zauna lafiya don Allah kin ji ko."
Jan bakina na yi na shiru na rabu dashi abinda dai na kudire a raina shine idan za ta ce zata yi mini hayaniya ko ta zage ni kaniyarta zan ci, tunda ga wanda ya yi mata nan
Ya dube ni a tsanake kafin ya ce." Na kira Anti Yagana a waya kan maganarmu dake ta d'azu."
Yanayin yadda ya yi maganar ya sanya ni jin sanyi a cikin raina, har ga Allah ina jin dadin yadda yake mutunta anti Yagana har ya sakaya sunanta.
Na nutsu Ina kallonsa.  Ya cigaba da cewa." Na amince za ki je amma da sharad'in kwana uku kacal za ku tafi a jirgi ke da Yusi da Sukairaju nasa a yi muku shirin hakan, kada ki sa'ba umarnina."
Da sauri na ce." In sha Allahu na gode sosai Allah Ya kara girma." Ya amsa da "Amin." Kafin ya cigaba da cewa." Ni ma yana da kyau na bada gudumawa ko."
Murmushi na yi ban ce komai ba.
Ya ce." Nawa ki ke ganin zan basu."
Na dube shi sai na dan ji tausayinsa, shi dai abin sa bai rufe masa ido ba.
Na ce." Ko nawa ka basu sun gode."
Ya ce." Ai shawara na tambayeki sai ki ce mini ka basu abu kaza."
Na ce." Wallahi ban san abinda zan ce maka ba.
Shiru ya yi yana lalube a wayarsa.
Shigowar sa'ko na ji a wayata dake gefana na d'auka ina dubawa miliyan goma ne.
Na dube shi cikin mamaki mai tsanani. A nutse ya ce." Ki cire miliyan biyar ki basu gudumawace ni dake. Miliyan biyar din kuma kudin yaranki ne wanda na yi muku alkawarin satikan da suka wuce ba ke kadai na bawa kuna da yawa.
Na ce." To ai ni ban ce ina neman hakki ba."
"Idan ba ki ce ba yaran fa?" Ya fad'a yana kallona.
Na ce." Ni dai gaskiya dawo maka dasu zan yi wallahi.
Ya mike yana fad'in." Ki dawo mini dasu sai ki ga 'bacin rai, ki ajiyewa yaran zasu amfana anan gaba in sha Allahu, kuma koda jita jita zata  sake tashi a gari ba zasu zarge ni ba.....✍
*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen  gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari  ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*

*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*33*
Kawai sai na bi shi da Ido bakina ya yi nauyin da na kasa ce masa komai ya bud'e kofar d'akin ya fita.
Gari yana wayewa na kira Anti Yagana a waya muka gaisa sosai na ce." Ashe kun yi waya da maigidan."
Ta ce." Jiya ba ya kira ne domin karin bayani akan maganarku ai ya ce zaku taho gobe ma."
Na ce." E in sha Allahu anti Yagana amma don Allah don Annabi duk abinda na zo muku dashi kuyi mini kyakykyawar fahimta."

A sanyaye ta ce." Me Kuma ya faru?"
Na ce." Sai na zo din kawai zan miki bayani." Ta ce." Ni wallahi kin kashe mini garkuwar jiki Amina, ba fa na san fitina yadda mijin nan naki yake sonki me zai miki."
"Humm! Anti Yagana kenan akwai matsaltsalu sosai, ke ba za ki gane ba ne wani irin mutum ne."
Ta bata rai tana cewa." Kamar yaya wani irin mutum duk mazan fa haka suke Amina daga manya har yara, kin san Allah akan mutumin nan zamu 'bata."
A sanyaye na ce." Anti Yagana me ya yi zafi haka ni ce fa taki,
Ina ganin yana da kyau ki dubi uzurina."
"Ki gaya mini kawai yanzu ina jinki ba na so ki barni da damuwa a raina.
Ajiyar zuciya na sauke na ce." Anti Yagana kin san babban abinda yake lalata aure shine zargi ko?"
Ta ce." Kwarai kuwa."
Na cigaba da cewa." To shi wannan mutumin halayarsa ce, domin kuwa bashi da ta'ada mai kyau, ba na so tafiyarmu a haka ta ginu har tayi kwari, kin ga ina da kishiya ita kuma budurwa ya aureta. Ni kuma daga zarar mun samu sa'ba ni ya dinga ya'ba mini magana kenan, na auri maza biyu na yi harkar social media, ba ni da kunya ba ni da tarbiya, ina tallata surata a duniya zan 'bata masa suna maganganu da makamantan wad'annan, shine nake so manya su shiga lamarin nan dan gaskiya akan wannan wallahi a shirye nake da na rabu dashi."
A dan sanyaye ta ce." To me yasa ba ki gayawa Babanmu ba."
"Anti Yagana mutumin nan baya ganin girman Babanmu kin san ba wani girmansa ya yi da yawa ba yana ganinsa haka, shi ma kuma Baban namu ba zai iya tararsa da maganar ba, balle kuma Baba Sule."
Ta ce." To nan din idan ki ka zo wa za ki gayawa?"
Na ce." Anti Yagana ko ke ba za ki iya yi masa magana ba."
Ta ce." Na ce masa me? Amina ni kwarjini yake yi mini wallahi."
Na girgiza kaina tare da cewa." Shikkenan anti Yagana sai na zo din sai mu sake tattauna maganar.
Jikinta a sanyaye ta ce." To shikkenan Allah Ya kawo ku lafiya.

Baban Saude shine na biyu a gidansu Mamanmu mutum ne mai zafi da rashin san wargi, a iya tunanina shi kad'ai zan iya gayawa matsalata ya yi mata duban tsanaki, kuma ya tsage gaskiya duk d'acinta. Yadda na fahimta kwata-kwata ba zan samu goyon bayan anti Yagana ba domin gabad'aya mutumin nan ya gama dabaibayeta da alherinsa. Ba ita kadai ba ma kusan da wahala na samu goyon bayan duk wanda zan gayawa korafina akansa shiyasa sam ban tunkari Babanmu ba saboda na san zai tankwarani ne kawai ya ce na yi hakuri ko da kuwa ya duba maganartawa da k'amshin gaskiya. Anti Yagana tafi sha'kuwa da dangin Mamanmu tunda ita a can ta girma har ta yi aure, ni kuwa ban shaku dasu sosai ba domin har yanzu wasu daga ciki ma ban gama saninsu ba tunda gaskiya suna da family mai girma, shi kansa Baban Saude sai a shekarun baya na waye dashi domin matafiyi ne duk zuwan da nake yi ba na ganinsa sai an yi katari ya zo gida tukkuna, bashi da

wasa ko kad'an kuma mutum ne mai dattako da sanin ya kamata, sannan kuma yana gaskiya dan ko hukunci za a yanke a family din akan ce a bari ya dawo.
Kudirin dana yanke kenan a cikin raina idan na je na huta zan ke'be dashi na gaya masa sai na ji abinda zai ce akan hakan don gaskiya duk mutumin da yake da hankali ya kuma san menene aure da zamantakewa ba zai dinga zargin matarsa ba Koda kuwa a gidan karuwai ya aurota.

Wannan maganar ita na sake jadaddawa anti Yagana bayan saukata a garin a kuma gidanta. Sai ta fusata ainun tana fad'in muddin za ta fad'a mini na ji to na janye tashin maganar nan a family domin abin zai zama abin gotsiri tsoma kowane aure akwai jarabawa a ciki, a cewarta muddin na ce zan dinga bankada sirrina kowa ya sani to a shirye wasu suke da su lalata mini aure, kuma don Baban Saude ya kashe mini aure ba abinda zai dame shi ba ne, tunda saboda tsaurinsa yaransa uku suna nan a zaune a gida suna zawarci saboda irin tijarar da yake yi wa mazajensu yau da gobe sun gaji sun koro su.
Na so na fahimtar da anti Yagana bafa nufina a kashe auran ba, a dai yi masa magana ya gyara kawai, ba zai yiwu ace don yana da iko ya zamana kowa yana shakkarsa ba, duk abinda ya aikata daidai ne ko da kuwa kuskurene. Na san ta san gaskiya kawai tana takewa ne dalilin dabi'unsa na bayyane kafewarta akan hakan ta sake tsamari da na gaya mata adadin kudin da ya bada gudumuwa sai ta kara jajurcewa kan cewa ba da yawunta a tozartashi ba.
Ni kuma na san baban Saude ba zai yi masa magana domin ya bata mini aure ba sai dan gyara ko da take fad'in yaransa suna zawarci ban yarda saboda halinsa aka yi masa haka ba face kaddara domin kuwa yana kishin nasa ne bai yarda a wulakantasu ba. Mazan na yanzu sun riga sun zama abinda suka zama don ita Allah ya taimaketa tana zaune da nata lafiya lau ba zai yiwu a ce kowa haka yake ba.
Duk da na ha'kura na bi umarninta ba ta daina jin haushina ba motsi kad'an sai ta ja tsaki tana fad'in." Allah Ya rufa miki asiri kina so ki butulce masa ko Amina, ni ganau ce ba jiyau ba, mutumin kamar ya tsuguna miki saboda kulawa amma lallai sai kin kago masa lefi, to ya  ni ma ba zan ce kin fi sha'awar rayuwar tallata surar jiki ba, idan wasu ne suke rudarki wallahi za su kai ki su baro."
Na gaji dai na rushe da kuka domin tuntuni shi yake damuna, ta hana ni na yi magana kuma na hanu amma tana gasa mini bakaken maganganu. Na tashi na shige d'aki na kwanta ina kukan yadda zan yi.
haka aka yi shagalin bikin da ni cikin kunci domin duk yadda na so da na danne abinda yake damuna na kasa. Ni kaina ba zan so lissafin aure ba, to amma idan kaddarata ce hakan ya zan yi. Akwai fa matsaltsalu masu yawa dangane da zamana da mutumin nan amma ba kowane zai fahimci hakan ba.
Sai Babandi ya takura mini da tambaya domin shi ya yi mini farin sani bayan anti Yagana babu wanda yake saurin fahimtar damuwata sai su dalili ina da yawan wasa da barkwanci kuma koyaushe fuskata a sake take.

Matsanta mini da ya yi da tambaya ya sanya na dan tsakura masa kad'an daga cikin abinda yake faruwa
Ban ta'ba tsammanin zai fusata ba. Kawai ya dinga bala'i yana kumfar baki fadi yake yi Idan baya sonki ya sake ki mana akwai masu so da yawa shi bai san dami ya tsinta a kala ba.
Wannan ai jahilci ne ka auri mace tana zaune a gidanka kuma kana zarginta dan kin auri maza biyu kafin shi shine me? Wallahi ko yau ya sake ki ni zan aureki, idan ma kin ce ba kya sona akwai wanda zan hada ki dashi saurayi kuma mai rufin asiri, dama sautari auran masu kudin nan ba tomo ba ne.
Da kyar na sassauto dashi ya yi shiru sai huci yake yi abin ya dinga ba ni mamaki. A wurin kafin mu rabu na nuna masa cewa lallai dole ya boye mini sirrina ba na so kowa ya ji, shi ma na gaya masa ne domin ya ba ni shawara, dan idan ya fasa maganar kowa ya ji mai raba ni da anti Yagana sai Allah.
Illai kuwa duk kaffa kaffan da nake yi sai da ta tsargu ganin mun fito daga storoom din gidan tare muna magana tana cikin jama'a amma kaf hankalinta yana kanmu..
Gabad'aya jikina ya yi sanyi na wuce na karbo abinci cikin fulas na nemi Yusi dake can cikin yara na bashi ya kaiwa Sukairaju can gidan anti Yagana tunda tare muke ya zame mini jela duk inda zan je yana bina a baya bisa bin umarnin ubangidansa. Gidan bikin ne na ce masa ba na so ya biyo ni kawai ya zauna zan aiko masa da abinci shi ma ba a son ransa ba sai da na hada da fad'a tukkuna.

Muna komawa anti Yagana ko ta bari mu huta ta fara surutai. " Idan Babandi ya zugaki kike kashe auranki Amina bai wuce shi din ya aureki ba tunda na gane dama tuntuni yana sonki bai fad'a ba ne sai yanzu, to me na sama ya ci balle ya bawa na k'asa. A yadda kike Amina ai sai irin su Alhajin Tajon din, shi din ma sai dai Allah ya k'wace shi, amma muddin Babandi ya aureki sai ya gane shayi ruwa ne shege yana yawo da bakar fuska.
Duk da kuncin da nake cikin sai da na yi dariya na ce." Anti Yagana ina da wani mugun hali ne da za ki ce haka, ni fa abinda kike zargi ba shi ba ne, kin san dai Babandi mutumina ne ko?"
Ta share ni ba ta ce mini komai ba, amma motsi kad'an za ta yi kwafa ta girgiza kanta tabbacin abin yana damunta. Sai ta ba ni tausayi domin na gama fahimtarta ita dai kokarinta ta danne ni na zauna saboda kada duniya ta zage ni, a kuma yi mini lissafin aure shine kawai abinda take gudu.
Da daddare misalin goma da wani abu ya kira ni a waya. Dama tunda na sauka a garin sau d'aya mukayi waya kuma shi ya kira ni. Ina sane na ki d'agawa har sai da ta katse ya sake kira ta katse a k'alla sai da ya kira sau hud'u na daga ina sallama.
Ya ce." Wanene Babandi?"
Gabana ya buga da karfin gaske! jin sunan Babandi a bakinsa. Da kyar na daure na ce." 'Dan uwana ne."
"Shine kuka 'keba a wajan da babu gilmawar mutane? idan dan'uwanki ne me zai sanya ba za ku tsaya a bainar jama'a ba."

Na daidaita nutsuwa sosai domin yin hakan shi kadai zai kwace ni daga mummunar zarginsa. Shin a ina ma ya san na yi hira da Babandi.

Don girman Allah ki tausaya mini ki biya ni hakkina idan har kina karanta wannan littafin kada ki bari hakkin wani ya kamaki.

"Anan din ma sai ka tuhume ni akan abinda baka da hujja wai dan girman Allah a gidan karuwai ka auro ni Baba, ko kuma dai ka fara tu'ammalli da muggan kwayoyi da suke fad'a maka karya da gaskiya."

"Kina mamaki ne don na tuhume ki, ki ba ni amsar tambayata kawai idan har Babandi dan'uwanki ne na jini me zai sanya ki 'kebe dashi shi kadai, daga barin ganin idanun jama'a, idan 'yan uwantakar ta gaskiya ce mai yasa ba za ku yi hirar a kan idanun jama'a ba."

"Saboda akwai muhimiyar maganar da muka tattauna, Babandi Kuma d'an'uwana ne na jini tunda iyayenmu cikinsu d'aya, kuma tun kafin na sanka nake tare dashi wannan shine bayanin kawai da zan iya yi maka a kansa."

Kashe wayarsa ya yi ba tare da ya sake yin wata magana ba. Jikina a mace na ajiye tawa wayar ina tunanin yadda aka yi ya san na ke'be da Babandi. Sukairaju anan gidan anti Yagana na bar shi. Na san kuma ko giyar wake anti Yagana tasha ba zata gaya masa ba tunda ita kokarinta ma na koma gidana na cigaba da zama.
Yusi ya shigo d'akin da nake da yaran 'yan uwa dana anti Yagana na ce su je waje domin lokacin k'wa'kwalwata tana buk'atar hutu.
Suka juya zasu fita na kira shi ya dawo shi kadai na ce." Kun yi waya da Baba ne a wayar Sukairaju?"
Da sauri ya ce." Eh d'azu da na zo kawo masa abinci na same shi suna waya shine na ce ya ba ni shi mu gaisa."
Gabana na dan bugawa ba ce." Kai ne kenan ka ce masa ka gan ni tare da Babandi ko.....✍
Jama'a an jangwalo mai neman kuka😩
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN✍*

TEEMAH DATA SERVICES MTN

1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*

*Da zumarta*
*Sabaya ce  dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*34*

Ya gyad'a kansa yana ce wa." E, tambayata ya yi kina Ina shine na gaya masa kina can tare da Babandi a storoom."
Na zuba masa ido ina ji kamar na gaggaura masa mari saboda takaici!
Ganin irin kallon da nake yi masa ne ya sanya jikinsa mutuwa sai ya sunkuyar da kansa da kyar na ce.'' Jeka ku kwanta dare ya yi."Ya kama hanya ya fita ba karsashi.
Cikin baccin da ya fara fizgata na ji tana kirana na tashi zaune da sauri Ina kallonta
Tana cikin kayan bacci don wata'kila ma daga turakar mijinta take ta kufto ta fito saboda rashin ha'kuri ganinta a hargitse ya tabbatar mini da cewa ta san abinda ya faru wata'kila ma shi ya kira ta ya gaya mata.

Kada ki karanta mini littafi ba ki biya ni hakkina ba yar uwa.

"Kina ganin abinda kuka yanke da Babandi shine mafita a rayuwarki Amina."
Na dube ta a tsanake na ce.'" Anti Yagana me muka yanke ban fahimci inda maganarki ta dosa ba."
Ta gyada kanta cikin takaici da jin haushi ta furta." Yanzu Amina a ce kamar Babandi shi ki ka bawa lasisi da ragamar auranki saboda kin zama mara mafadi babu wanda ya isa ya gaya miki ki ji, a ce wai Babandi shine zai tsara

miki yadda za ki yi, Kuma ki bashi kwarin guiwa da hadin kai ya kira mijinki mutum kamar wannan da yake da kima da dattako da shekaru ya gaya masa maganganu masu kaushi, ashe Amina ni ban isa na gaya miki magana ba ko?"
Sai kawai naga kwalla ta ciko a kwarmin idonta.
Hankalina ya tashi sosai na ce." Wallahi tallahi anti Yagana ban yi haka da Babandi ba, ya takura mini da tambaya ne shine na dan tsakura masa abinda yake damuna, kuma na gargadeshi akan kada ya gayawa kowa, ban taba tsammanin ma zai iya kiransa da wata magana ba, a Ina ma ya samu lambarsa mutumin da ba kowa ya san lambarsa ba.
Hawaye suka keto kumatunta suka fara d'iga.
Sai na ji duk gwiwata ta sanyi me ya yi zafi Anti Yagana take kuka irin haka.
Hawaye suka silalo mini na ri'ke hannunta ina fad'in." Wallahi tallahi anti Yagana ban sa shi ba, ban san a inda ya samu lambar wayarsa ba, ki gaya mini abinda ya fad'a masa domin tunda naga kina kuka na san abin babba ne."

Ta goge hawayen tana cewa." Ni babbar damuwata shine duk rintsi duk wahala ki yi hakuri ki zauna a dakinki Amina, ba wai na kafe akan don mutumin nan yana da wata suttura ba a a ke nake dubawa da kuma yaranki, matsalarsa ba mai muni ba ce a ganina tsananin so ne yake janyo kishi shi kuma na fahimci duk lokacin da zai tuna maza biyu sun taba ki kafin shi yakan kasa sarrafa kansa. Kishin maza fa daban yake dana mata wallahi maza sun fi mata kishi, mu hauka muka fi su. Kada wani ya rudaki akan ki fito ki yi hakuri ki zauna domin Babandi ba zai ta'ba iyawa da bukatunki da na yaranki ba. Karshe dai ki kara famtsama harkokin da ki ka bari a baya."
Ina kuka na ce." Na ji batunki anti Yagana Kuma na fahimci duk abinda kike nufi, ni kaina ba na so ace na fito daga d'akina, amma abinda nake so ki fahimta shine, bayan wannan matsalarfa akwai wata a kwance nasan baki manta da cewa samun haihuwa zai yi mana mutukar wahala a tsakaninmu ba duba da sakamakon gwaji da abinda ya faru a baya na rasuwar abinda muka haifa.
Akan iya samun matsalar haihuwar yara marasa lafiya tunda har jini ya nuna anti Yagana kuma kinga ni duka yarana biyu a duniya, shi kuma a yanzu ne yake da buk'atar tara zuria. Haihuwa da wahala tun daga samuwar cikin raino da nakud'a. Ba fata nake yi ba duk na gama shan wannan wahalar Kuma na zo na haifi da mai lalura daga karshe ya mutu, anti Yagana akwai ciwo da damuwa wata ta zo daga bayanka kana kallo ta yi ta haihuwa kai kana zaune."

Ta girgiza kanta cikin damuwa ta furta." Na gaya miki tun farkon lamarin nan ki k'adaita Allah, domin su kansu turawan da suka kirkiro abin nan hasashe kawai suke yi, babu fa wani mahaluki da ya isa ya canzawa Allah manufa duk abinda ya wanzar shine daidai. Ki saki zuciyarki ki zauna a dakinki, idan za ki haifi yara goma su mutu dama haka Allah ya nufa, idan kuma zaki haifi yara goma su rayu haka Allah ya nufa. Ai Kinga da za ki auri Aminu ba a yi gwaji

ba, kuma gashi kin haifi yara masu lafiya kwarai da gaske, to wannan ma kadai ya isa ki barwa Allah abinda ya tsara miki"

Ni kukan da take yi shi ya fi daga mini hankali domin na jima ban ganta cikin yanayi na damuwa da tashin hankali ba, kukanta yana da ala'ka da abu biyu domin yau yini aka yi a gidan bikin nan ana hirar Mamanmu  har wasu daga cikin 'yan uwanta suka dinga kuka, a ganina matsalata kadai ba za ta sanyata zubar da hawaye irin haka ba, tashin zancen Mamanmu da 'yan uwanta suka yi shi ya kara dagula mata lissafi sai ni ce na yi namijin ko'karin tsayar da nawa hawayen na dinga rarrashinta akan ta yi shiru ban samu hakan ba kuwa sai da na yi mata al'kawarin duk rintsi da wahala zan  ha'kura na zauna a d'akin mijina
Da wannan alkawarin ta tashi ta fita ta barni cikin tunani da zullumi. Ni dai nasan anti Yagana ba makwadaiciya ba ce balle na ce mutumin nan siyanta ya yi da kudi. Na fi zargin dai abin a jininsa yake domin na fahimta duk wanda zai yi mu'amula dashi da wahala ya hangi kuskuransa. Ni a karan kaina  na san shi din mutum ne domin kuwa duk inda ake neman dattako da nagarta taimako da tausayi ya kai a jinjina masa. Amma a dabi'a da halayya irin ta dan adam  dole a same shi da wani nakasu wanda sai mu da muke zaune dashi za mu tabbatar.
Baya ga mummunan zarginsa babu komai a tsakanina dashi face alheri domin har yau har gobe ina kallonsa da hakan, amma ina ji a cikin raina zamanmu ba zai yi dad'i irin yadda anti Yagana take so ba muddin bai canza dabi'a ba, ni kaina ba wai so nake a ce mun rabu ba domin duk abinda take yi mini hange ni ma ina yin hagen haka, to amma ai zaman ba zai yi tasiri ba idan da cin zarafi a ciki.

Kamar yadda ta ce mini na kira shi na bashi ha'kuri bayan wanda ta bashi ban ce to dan na yaudareta ba na yi aniyar kiran nasa sai dai fargabata ban san irin martanin da zai mayar mini ba tunda na gama fahimtarsa bai iya b'acin rai ba.
Sha biyu da wani abu idona biyu na kasa rintsawa saboda fargaba da tunanin d'anyan kan da Babandi ya yi mini, kawai don ina jin nauyinsa ne ya sanya ni dannewa amma tabbas da wani ne ba zamu wanye lafiya ba. Wayata na d'auka wadda  har na kashe na ajiye zuciyata ta kasa nutsuwar barin gari ya waye na kira shi, na san yanzu da wahala idan ya kwanta ya kan kai karfe daya yana aiki da computer kafin ya kwanta.
Da fargaba na lalubi lambarsa na kira hannuna na dan karkarwa karon farko kenan da nake jin fargaba da tashin hankalin wani raddi daga wajansa.
 Sai dai kuma daga zarar wayar ta fara shiga sai ta katse. Na tashi na fita falo wai ko network ne nan ma ta dinga yankewa, ni ce dai har farfajiyar gidan amma ta'ki tafiya.
Babu kuzari na koma daki na zauna da wayar a hannuna na rasa wane nazari zan yi. Kai tsaye dai ba zan yanke masa hukunci ba, amma ai ban ta'ba kiran layinsa ya yi mini haka ba.

Ban ha'kura ba na jarraba kiran Sahura sai gashi ta shiga har ta fara ringing na katse da sauri na sake nemo lambartasa a karon da babu adadi ta sake katsewa. A lokacin na gazgata hasashena a busy ya sanya ni. Bai d'auki waya ba na san ko text na tura masa ba zai duba ba tunda dama can ya kan tara messages na mutane kafin ya samu damar dubawa.
Na kwanta cikin zullumi da tunani lallai akwai maganganun da Babandi ya gaya masa dama ai mai neman kuka ne aka jefe shi da kashin awakai yanzu shawo kansa sai na kusa zama k'aramar mahaukaciya.

Ban ta'ba kawowa zuciyata saki a cikin irin hukuncin da yake ganin zai yi mini ba, domin ni kallon da nake yi masa ma kome zan yi masa na takaici ba zai d'auki matakin sakina ba sai gashi na wayi gari da ganin text dinsa na saki d'aya Inda ya rubuta a takaice da kuma babban hafarai "NI ALHAJI TAJUDDEN IBRAHIMU NA SAKI MATATA AMINA SALISU SAKI DAYA." Na yi bala'in kad'uwa daganin sakon gabana ya dinga bugawa da mugun karfi yayin da wani irin yawu ya tsinke mini a bakina.
Da kyar bakina ya kar'bi abinda zuciyata take amayowa na dinga nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Zuciyata na harbawa da mugun karfi. To da yake babu abinda ya fi ambaton Allah samun sasaauci a lokacin dadi da b'akinciki, cikin kan'kani lokaci na dan shiga nutsuwata na fara tunanin yadda zan yi na shawo kansa ya mayar da ni ba tare da kowa ya ji ba.
Babbar damuwata Anti Yagana da alkawarin da na yi mata jiya kafin ta je ta kwanta, amma ni idan ta ni ce zan iya jurewa tunda ba shine karo na farko ba. Har yanzu zuciyata ta'ki aminta da cewar da sanin mahaifiyarsa ya sake ni. Ya yi mini hakan ne saboda ya nuna mini ni din ba komai ba ce. Kishi ba hauka ba ne yana da kyau ya ji ta bakina kafin ya d'auki d'amarar tozartani.
Hawaye masu zafi suka kece mini suka fara kasa tsere a dakalin fuskata.
Na yi kasa'ke da waya a hannuna gwiwata ta sage tamkar an buga mini guduma, komai ya dagule mini na rasa ma abinda zan yi.
Shi din zan nema domin na ji ba'asi akan abinda ya yi mini, har yanzu ban yarda da cewa abinda na aikata na cancanci hukuncin saki ba, ai ba rufe kofa na yi da Babandi ba, sannan kuma duk abinda zuciyarsa zata kitsa masa a kaina bai gani da idonsa ba, ni ba mazinaciya ba ce, idan ma yana hasashen hakan a kaina.
Na kira shi ya fi sau goma sha biyu bata shiga. Hawayen nadama da tausayin kaina suka dinga gudana a kumatuna. Ba zan kira mahaifiyarsa na na gaya mata ba, domin na tabbatar da cewa ba ta san abinda ya faru ba domin da yawunta ba zata bashi goyan bayan yi mini wannan tozarcin ba. Sannan bata da koshin lafiya Ina ganin jin wannan labarin zai iya daga mata hankali har ciwonta ya tashi.
Garin Allah ya waye sosai haske ya fito ban fita ba asalima ban tashi daga kan daddumar da na yi sallar asubahi ba. A hakan anti Yagana ta shigo ta same ni ganina a rikice ya sanya ta zo ta tsaya a kaina tana tambayata.
Koda na dubeta sai wani sabon hawayen ya k'wace mini. Na d'auki wayata dake ajiye a gefe na mik'a mata.

Tana dubawa tana salati sai ta silale rigijib ta zauna  a gefena. Na rufe fuskata da hannuna  ina  kuka na furta." Anti Yagana ko me na yi wa mutumin nan ban cancanci wannan cin zarafin ba. Wallahi tallahi ba da hannuna Babandi ya kira shi ba, kuma dana san abinda zai faru kenan dashi kansa Babandi ban gaya masa komai ba. Anti Yagana ki duba lamarin nan a tsanake akwai izza da iko da nuna kowa ba komai ba ne a cikin sha'anin wannan mutumin ya iya taku ne shiyasa ba kowane zai fahimci hakan ba, amma menene lefi don an ce gyara kayanka, abinda fa yake aikata mini kuskure ne, na tabbata ko giyar wake Babandi yasha ba zai zage shi ba karshen dai rashin kunya kenan, magana ce ake yi akan dabi'ar da yake yi ba mai kyau ba ce, kuma duk wanda ya san ciwon kansa ya kuma san illar zargi a sha'ani na aure ya san hakan ba daidai ba ne, menene abin saki a nan anti Yagana don yana da wata alfarma wallahi ba zan bari ya wulakanta ni ba.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal what'sapp Gruop kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*

*Cibiyace da tai fice wajen  gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari  ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har  Madiga  tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma,  dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce  dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*

*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye* +2348032089456

*35*
Anti Yagana ta ja hanci idonta da sauran hawayen da ta gama gogewa ta ce.''Wallahi tallahi sai da na ji haka a jikina Amina, shiyasa fa jiya kafin na fita na umarceki da ki kira shi ki bashi ha'kuri kuma ki shanye duk b'acin ran da zai k'unsha miki, dan kyautawa ke da Babandi baku kyauta ba, kuma tun a jiyan na kira Babandi na tambayashi yadda suka yi dashi ya ce ya yi masa magana ne akan abinda ki ka fad'a masa har ya kara da cewa dashi bai auro ki a gidan karuwai balle ya yi togaciya da kiranki da wata kalma ya kara da ce masa harkar social media da ki ka yi kin yi ne domin rufawa kanki asiri da yaranki, ni dai iyakacin abinda ya fad'a mini kenan ban sani ba ko ya rufe wata maganar wadda ya gaya masa ta fusata shi ni bai gaya mini ba.
Kuma ko jiyan da muka yi waya dashi wallahi ha'kuri na bashi akan hakan kuma ya nuna mini ya ha'kura magana ta wuce amma hukuncin da ya yanke ya yi tsauri bai kai ga a ce an yi saki ba.
Na ce." Anti Yagana ki kyale shi kawai dan Allah dan annabi kada ki kira shi akan  neman hujjar da ya sake ni. Na san bashi da ita zai bata miki lokaci ne kawai hujja dai ita shi mai kudi ne, kuma ni ba kowa ba ce a wajansa a yanzu."

Idan har kina karanta littafin nan to ki daure ki biya ni hakkina kada ki bar kan ki da nauyin Wani.

Ta dube ni jiki a sanyaye." Ni fa Amina na fara zargin lamarin nan naki anya babu sa hannu a ciki, mutumin nan fa wallahi yana sonki ba zai iya sakinki cikin hayyacinsa ba wata'kila ana dan birkita masa tunani shiyasa ke din ma ya kasa aminta dake yake tsiro da abubuwa daban daban.
Shiru na yi ina nazarin maganarta. Zan iya gazgata maganarta tunda na gani da idona a lokacin da inna Uwani take yayyafin rubuta a wajan benansa. Amma idan ma da asirin to tabbas akwai hali da kuma dabi'a.
Ta shi ta yi zata fita duk ta ki'dime tana daf da kofa na kira ta a nutse na ce." Anti Yagana don Allah kada ki kira mutumin nan a waya dan Allah ki yi mini wannan alfarmar."
Ta ja ta tsaya tana dan kallo kafin a sanyaye ta ce." To ai yana da kyau a tambaye shi dalilinsa ko."
Na ce." Dalili da ba zai wuce abinda na gaya miki da farko ba. Kishi zargi giyar kud'i."
"Amma dole mahaifiyarsa ta san da abinda ya faru Amina, domin bahaushe yana cewa ta inda aka hau ta nan ake sauka."
Na ce." Itama din ba za ta ji daga bakinmu ba shi ya fad'a mata. Ni dai tsorona ma kada wata magana ta fita duniya ta ji na shiga bakin duniya kin

san shi sha'aninsa a waje yake motsi kad'an manema labarai za su fara watsawa shine babbar damuwata kuma kin san yadda da dama mutane suke yi wa macan da take gudanar da harkokinta a internet ko da bata aikata komai halalinta take nema sai a juya mata manufa a yi ta jifanta da bakaken magana."
"Babu abinda zai faru in sha Allahu ma ina fatan kafin zuwa gobe ya mayar dake shikkenan babu wanda ya ji ya kuma ga ni." Tana gama maganarta ta fita daga d'akin a gaggauce.
Ban fita ba tukkuna sai da na yi wanka da yake da bandaki a cikin d'akin na kimtsa jikina abin yana ta sasakata a zuciyata ina dannewa idan takaici ya yun'kuro mini sai na ambaci Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Da kyar na iya kurbar shayi ban iya hadawa da borodi ba saboda lami nake jin bakina. Anti Yagana ta fito cikin shiri zata fita na ce." Ina kuma za ki je"
Tana gyara gilashin da yake idonta da yake tana da dan matsalar Ido wanda yasa asibiti suka yi mata gilashi take amfani dashi idan zata fita ta ce. " Ba zan ji ma zan dawo kafin azuhur."
A cikin raina na ji cewa saboda matsalata zata fita.
Na ce." Anti Yagana ban san ki da biye  biyen malamai ba don  Allah kada ki fara akan wannan karamin dalilin, kada ki yi wasa da tunaninki, ni dake mu zauna mu tattauna abinda zai taimake mu. Nasan akan duk abinda ki ka tashi hankalinki, amma ki sani kowane bawa yana tafiya ne da kaddarsa, kuma mutumin nan bashi kadai ba ne namiji akwai su da yawa, idan Allah Ya kaddara mini sake wani auran nan gaba sai ya had'a ni da wanda ya fishi.
Jikinta a sa'bule ta ce." Da wai zuwa zan yi a yi mini istahara ta musulunci Amina, idan kuma da dan wani taimako ko rubutu ko hayakin da za a baki sai ki yi amfani dashi domin sake janyo hankalinsa tunda dai ni na tabbatar da cewa mijinki yana sonki."
Murmushin takaici na yi na ce." Anti Yagana ai maganar so da k'auna ta kare tunda har ya sake ni, ni dai abinda nake so ki samu nutsuwa don Allah mu barwa Allah."

Ta gyada tana dan nazari kamar ta d'auki maganata sai kuma a zabure ta daga labule zata fita take cewa." Bari dai na dawo ai na san irin malaman da zan je wurinsu.

Ina nan zaune ina sa'kawa da kwancewa Sahura ta kira ni a waya tana bin ba'asin kiran da na yi mata cikin dare kawai sai na ce mata mistake ne ni ban san ma na kira t ba sai yanzu da ta yi magana. Muka dan ta'ba hira kad'an kafin mu yi sallama. Na kira Yusi na tambayeshi akan kaiwa Sukairaju abin kari ya ce mini tun d'azu.
Na sauke ajiyar zuciya tare da bashi umarnin tafiya har ya juya kuma sai ya tsaya yana tambayata wai yaushe za mu tafi tunda yau kwananmu uku haka baba ya ce mu yi kwana uku.
Rashin amsar da zan bashi ya sanya na ce ya fita ya ban waje. Ya kama hanya ya fita jikinsa ba kuzari. Ni yadda ma zuciyarsa zata manta da shi

kawai nake ji, na lura da irin wannan  sha'kuwar ce take sanya mutum  ya kwanta ciwo idan an rabu.
Wai saki ni abin ma mamaki yake ba ni, hakika lamarin ya kidima ni.

Wajan shad'aya  da rabi anti Yagana ta dawo a gajiye ta zauna a falo. Na zuba mata ido tausayinta na ji yana tsirga mini duk wannan fad'in tashin akaina take yi da kud'inta da ga'bobinta.
K'walla ta ciko kwarmin idona amma ban yarda ta zuba ba na yi c
'kok'arin mayar da ita Ina kallonta tana fito da kayan dake cikin jakarta ta ce." Ina hanya sai ga wayar Babanmu wallahi lokacin da ya kira ba ki ga yadda hankalina ya tashi ba domin na yi tunanin mijinki ne ya gaya masa abinda yake faruwa, wai ashe Hadiza ce za ta tafi dubai saro kaya shine ya ce wai na kira ta na yi mata magana domin shi fa idan da yawunsa ne bai amince a bar 'kasa da zummar neman kudi ba."

Cike da mamaki na ce." Dubai uban me zata saro a can din, a ina kuma ta ga jarin da har za ta yi visa ta d'unkule kudi ta tafi wata kasa."

Girzgiza kanta ta yi da takaici mai yawa a tare da ita ta ce." Ni ma tambayar da na yi masa kenan ya ce shi ma bai sani ba amma ya fara zargin mijinki ne ya bata domin Ummansu Saminu ta ji su suna maganar watarana bayan ta dawo daga unguwa suna d'aki ba su san ta shigo gidan ba. Bayan miliyan shidan da ta yi k'arya da rashin lafiyar Fati ta kuma tambayarsa kudi."

Takaici da b'akinciki ya hana ni cewa komai. Har da hadi'n gwiwar  hadiza wajan ko'karin wulakani da mutumin nan yake yi.
Anti Yagana ta cigaba da cewa." Kwanaki da na yi mata magana akan me yasa suka shirya karyar ciwo don su kar'bi kudi wallahi ba ki ga rashin kunyar da ta yi mini ba, shiyasa ai na cewa Baban namu ba zan iya cewa komai ba akan Hadiza  ba domin tana samun d'aurin gindin uwarta ne."
Zuciyata na zafi na ce." Anti Yagana yanzu dan Allah wannan shine daidai ne, Hadiza fa ta wulakanta ni a wurin mutumin nan, ta zubar mini da mutunci, me yasa ba zai nuna ni ba komai ba ce, ya san ba ma shiri har da sakamakon saki mai zai sanya ya tura mata kudi."
"Ni kaina raina ya 'baci to babu wata dama ta gyarawa ya riga ya faru kuma kin ce mini shine ya bata damar yin hakan baki da hujjar yin wata magana kud'insa ne."
Hawayen dai da nake dannewa suka zubo a kumatuna na ce." Amma dai ai bai dace ba, fad'a fa muke yi  me yasa zai tura mata kudi, yadda yake jin haushina akan lefin da bashi da tabbas ya kamata ace ya k'yamaci duk abinda ya shafe ni."
Murmushi ta yi tana cewa." Wani sa'in fa maza sun fi mata kaidi Amina, ba ta yadda za a yi fa ki fito a yanzu ki nuna wannan bawan Allah ba ya kyauta miki mutane su yarda da maganarki, yana amfani da dukiyarsa ne wajan sayan al'umma bisa la'akari da yadda rabin mutane suka zama makwadaita. Babanmu da sauran 'yan uwansa ba zasu ta'ba yarda da maganarki ba

wallahi. Ban 'ki  ba Baban Sauden  ni kaina yanzu na fara hasashen halayensa marasa kyau da yake b'oyewa mu kuma yana bayyana mana masu kyawu amma idan ba haka ba me zai sanya ya san da wannan rikicin a tsakaninku ya d'auki kudi masu yawa ya bawa 'yar uwarki, ya shirya kai ki kasa ne koda maganar ta fasu babu wanda zai aminta dake "

Hannu nasa na goge ragowar hawayen da yake fita daga idona yayin da nake jin wani irin zugi a kasan zuciyata. Mutumin nan karshen munafiki ne.
Ta ce." Kin ga ba wai naki yarda da abinda Allah ya kaddara ba ne, amma kin san istahara gaskiya ce Amina, an bincika mini sosai lamarin nan akwai sa hannu tunda ai farkon auranku ba haka yake ba, tunaninsa a rikitar ana so ma adasa masa kiyayyarki da zarginki a cikin zuciyarsa. Yanzu haka ma malamin ya ce mini yana can hankalinsa a tashe domin lokacin da ya yi sakin a tunzure yake k'wa'kwalwarsa tana ta gaya masa karya da gaskiya yanzu kuma da ya dawo nutsuwarsa ya fara nadama."

Murmushin takaici na yi na ce." Anti Yagana duk wata istahara ta bi bayan wadda kai za ka yi da kanka, idan kin ce akwai asiri ko farraku a tsakaninmu ba zan musanta miki ba, amma ban yarda da cewa yana can hankalinsa a tashe ba me yasa bai kira waya ba."
Ta ce.'' Ai yanzu akwai turaran da za ki yi wanda dolensa ya neme ki kafin nan kafi faduwar rana haka malamin ya ce."

Dariya ce ta k'wace mini duk da halin da nake ciki amma yadda anti Yagana ta hakikance tsakaninta da Allah sai ta ba ni tausayi da dariya na ce." Anti Yagana ki yi hakuri ba zan iya hayakin komai ba indai akan bawan Allan nan ne, mu yi addu'a kawai idan da alheri komawata gidansa sai na yi hakuri na koma, idan kuma babu alheri sai ki ga Allah ya kawo mini wani.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram.Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700

CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*

*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*37*

Ya fad'a muryarsa har tana rawa, sai ya ba ni tausayi ni ma na ji idona ya ciko da kwalla dama daurewa kawai nake yi.

Haka muka karya a daddafe har yaran suma gabad'aya jikinsu ya yi sanyi ganin yadda muke cikin alhini da damuwa Yusi dai ya takure a kusurwar kujera har da kuka sai da anti Yagana ta rarrashi tukkuna ya yi shiru.
Garba almajirin anti Yagana ya shigo ya ajiye robarsa a bakin kicin ya shigo falon muka gaisa anti Yagana ta ce ya yi maza ya zuba ruwa a diro amma kafin nan ya fara wanke shi. Har ya juya zai fita sai ya tsaya yana kallon Yusi ya ce." Ka je in ji wannan din nan yama sunansa?" Ya tsaya yana tunani. fadila ta ce." Bak'on da suka zo tare?"
Da sauri ya daga kansa yana cigaba da cewa." E shi ya ce na kira shi yanzu ya je Babansa ya kira waya za su gaisa."
Na dubi Yusi da mamaki a tare da ni, dama duk safiya Yana kiran waya don su gaisa, da farko da Garba ya ce ya je na d'auka Sukairajun yana buk'atar wani abu ne bayan karin kummalon da aka kai masa.
Yaron ya tashi da saurinsa sai na dakatar dashi ina fad'in." Yusi dama Baban yana kiran waya ne ku gaisa kullum?"
Ya ce." E wataran ma har ya ce na bawa su Arif da Sultan su gaisa, ko Arif?"
Ya fad'a yana kallonsa. Ya ce." Eh hakane har ya ce a gaishe daku bakidaya.''
Na gyada da mamaki fal a tare da ni. To shin wai me mutumin nan yake nufi ne? Ni ban ma ga amfanin zaman Sukairaju a tare da ni ba, kuma yaro dai ni na haifi abina ba za a yi wannan munafurcin da ni ba, ka sake ni amma ka dinga bibiyar 'yan uwana har da yaron da na haifa da wani namijin.
Na ce ." To koma ka zauna ba za ka je ba."

Anti Yagana da sauri ta ce." Akan me?" Shiru na yi kawai Ina kallonta da mamakin neman dalilin da take yi wanda ta fi kowa sani.
Tana kurbar kunun gyadar da ta tsiyaya kofi ta ce." Ki kyale shi kawai ya je, idan kuma ba so kike ki fito da komai fili ba, ta inda ya fi ki wayo kenan, yadda yake tafiyar da lamarin a siyasance sai ki zuba Ido ki ga iya gudun ruwansa."
Na yi shiru Ina nazarin maganarta. Ni dai da ta barni zan datse alakar ne daga yau din, shi ma Sukairajun na sallameshi don ban ga amfanin zamansa a tare damu ba illa dorawa masu gidan nauyi da ya yi."
Kimanin minti ashirin yaron ya yi da fita sai gashi ya shigo ya zauna yana kallon anti Yagana ya ce." Baba ya ce na gaya miki zai kira ki yanzu."
Da sauri ta ce." To shikkenan Yusifa."
Kawai na saki baki ina kallon ikon Allah. Gabad'aya abincin ma da nake ci sai ya fita daga raina na zuba mata ido a lokacin da ya kirata suna magana akan rashin lafiyar Gwaggwo.
Anti Yagana ta saki jiki da baki tana ta jadadda masa yadda Gwaggwon take jin jiki har da ce masa tana kwance bata iya motsa komai na jikinta.
Da yake handsfree ta sanya wayar ina jin muryarsa tar yana cewa." Ni muna gaisawa da Yusuf na ji ya fashe mini da kuka koda na tambayeshi shine yake gaya mini kakarsa ce babu lafiya kukan yaron ya daga mini hankali kwarai da gaske dalilin da ya sanya ma kenan na kira ki domin na tabbatar ya gaya mini duk yadda aka yi, zan yi waya asibitin Malam din  duk abinda ake bukata game da mara lafiyar ba zai gagara ba idan ma gado za su bata hakan zai fi sauki Allah Ya bata lafiya."
Anti Yagana tana ta amsawa da Amin Ya Allah, mun gode sosai da kulawa Allah ya kara arziki da wadata."
Suka yi sallama ta juyo tana kallona raina a tsananin 'bace na mik'a hannu dukkunsu har shi Yusi din ba su ankara ba na kife shi da marin da na tabbatar zai gigita shi .

Kiji tsoron Allah idan har kin san baki biyani kudin littafina ba to kada ki karanta zai fi miki alheri ki ha'kura ko ki biya mai hakki hakkinta.

Illai kuwa a ki'dime ya tashi ya yi hanyar waje hannunsa dafa da kumatunsa hawaye suka fara kasa tsere a kuncinsa.
Anti Yagana ta rufe ni da fad'a tana fad'in." Sai kin je kin tsiyayar masa da ruwan ido haka kawai saboda zalinci zaki kifa masa wannan mugun marin me ya yi miki? Lefin dai ba zai wuce ya gayawa mijinki magana ba, shikkenan fa sai ki lahanta shi.''
Shiru na yi ban tanka mata ba kawai na tashi da zumar barin wajan. Yaron da yake tsaye a bakin kofa ya d'auka dukansa zan sake yi ya fita a guje yana sheshsheka.
D'aki na shiga na zauna a gefan katifa kaina a daure domin duk yadda na kai ga ganin na hasaso abinda mutumin nan yake nufi a kaina na kasa ganewa.

Shin wai ko ya manta da cewar ya sake ni ne, wane irin munafurci ne wannan da neman lallai sai ya d'ora mini lefi. Ka sake ni ka fita daga sha'anina mana.
Wayata na d'auka da sauri kiransa zan yi domin na ji shin me yake nufi da ni ne.
Kamar yana jiran kiran nawa karaf ya daga. A kaurare babu gaisuwa balle girmamawa dalili duk ya zubar da mutuncinsa a idona bana son mutum munafiki.
Na ce." Ban gane abinda kake nufi ba, ko ka manta cewa yanzu babu wata alaka da take tsakanina dakai? Ina ruwanka da bibiyar abinda ya shafe ni. Gwaggwo dai mahaifiyar mijina ce wanda mutuwa ta yi mana kutse ta shiga tsakani, na tabbata kuwa a duniyar nan ba zan sake katari da namiji mai nagartarsa ba. Kana ta bina da sharri, ka yi nan ka 'bata ni, ka bi nan ka 'bata ni, to ta Allah ba taka ba, ka ja tsumman rayuwarka, ba ma buk'atar ko kwabonka, ba na son munafurci ni."

Cikin nutsuwa kamar bai ji zafin maganganuna ba ya ce.'' Ai na mayar dake dama na yi ne domin ya zama gargadi a gare ki. Kuma ba don ke nake tsaye akan abinda ya shafeki ba, saboda wasu dalilai ne, ke ki ka haifi Yusuf amma ya fi ki hankali, kuma saboda shi  din na shiga lamarin, ai na san kakarsa ce ko ba itace ta haifi Aminu Salihi ba."
Cikin takaici da b'akinciki na furta." Ban mayu ba, wallahi ban mayu ba na saku har abada ni dakai dama can ba a son raina aka yi ba, ba zaka tozartani ba wallahi ko maza sun kare a duniya ba zan zauna da kai ba, kuma ko mutuwa Gwaggwo ta yi menene abinda ya dame ka, babu ruwanka ba na son munafurci fa." Na sake maimaita kalmar munafurci domin na tunzurashi.
Bai tunzuru ba a tsanake ya ce." Sai ki yi kuma ni dai na mayar dake shekaran jiya na yi sakin jiya da safe kuma na kudire a raina na mayar dake yanzu kuma na sanar miki, don haka har yanzu kina karkashin ikona."
 Da sauri ya yanke wayar kamar ya san abinda yake bakina mai muni ne tabbas da bai kashe wayarsa ba sai dai ya ji ruwan ashar a kunnansa  saboda yadda zuciyata take a tunzure. Na kasa motsi daga inda nake gumi na yanko mini tsabar tashin hankali kamar yadda ya fad'a a musulunce na mayu tunda ko jini daya ban yi ba kuma ka'idar musulunci jini uku ne na fita daga idda.
Hawaye masu zafi suka fara karakaina a kumatuna. Anti Yagana ta shigo d'akin da karsashinta ganin yanayin da nake ciki ya sanya ta d'an yi sanyi ta tsaya tana fuskantata..."Menene kuma?" Tambayar da ta yi mini kenan.
Cikin k'unci da takaici na ce." Anti Yagana a wannan karon dole ki yi hakuri na d'auki mataki da kaina domin siyarwa kaina mutunci. Yadda na lura da mutumin nan bashi da mutunci ko kad'an kuma yana yi wa mata kallon wulakantattu idan ba haka ba me zai sanya ka saki mace haka kawai babu hujja mai karfi saboda kawai jin dadi gobe kuma ka ce ka mayar da ita addinin bai ce haka ba Anti Yagana ki zauna ke kanki ki dubi lamarin nan a tsanake kada soyayyar da kike masa ta sanya ki danne lefinsa ba fa daidai ba ne abinda ya aikata mini."

Jiki a mace ta ce." Na sani wallahi Amina, kuma bayan ke wallahi tallahi babu wanda ya kai ni jin ciwon sakin da ya yi miki, ni yadda na fahimta kamar bashi da ilimin addini mai zurfi boko ce kawai take dawainiya dashi shiyasa yake ganin kamar abinda ya aikata ba wani lefi ba ne. Abu na gaba kuma kin san shi, abinda ba na sha'awar ya kasance da ni a rayuwata wallahi kema ba na sha'awar ya faru dake, ba na yi miki sha'awar zawarci da lissafin aure don ma Allah Ya takaita gidan alhji Muntari ba ki haihu ba, wannan dalilin ya sanya nake ta dannarki ki yi hakuri ki zauna kowace mace tana da kalubale."
Na ce." Anti Yagana kada ki ce na ki jin maganarki wallahi na fahimci abinda kike gudu, amma dai don girman Allah wannan karon ki kyale ni da mutumin nan kada ki shiga ciki ki ja bakinki ki yi shiru kawai ki zuba mini ido."
"To wane shiri za ki yi akansa kin san dai shi namiji ne ke kuma mace tunda kuma ya ce ya mayar dake bafa yadda za ki yi dole ha'kuri ne naki."
Na sani anti Yagana ba shirin da zan yi akansa amma ba zan koma ba kamar yadda yake tsammani wallahi sai ya tako kafarsa garin nan."
Ta gyada kanta tanà d'an murmushi ta ce." Abu ne me sau'ki ai tunda yana sonki za ki gan shi kuwa.
Ban ce mata komai ba har ta kama hanya ta fice daga dakin.

Tun cikin dare na kammala shirye shirye na don haka gari yana wayewa na fito a kintse da zummar d'aukar hanya tunda d'akin da nake yana da bandaki ban fito ba sai da na shirya tsaf tukkuna. Gabad'aya suna falon ana shirin karyawa hadda maigidan a zaune bai fita ba dama ba kasafai yake fita da wuri ba idan juma'a ce.
Fitowata ta d'auki hankalinsu gabad'aya na gyara yanayina don ba na so ta dakatar da ni daga kudirin da na yi. A tsanake na ce." Anti Yagana na shirya fa zan tafi kamar yadda muka yi magana jiya wallahi da Gwaggwo na kwana a cikin raina."
Tana kallona ta ce." To kin gayawa mijin naki ko dai ?"
Eh kawai na ce mata a takaice. Yadda ta zuba mini ido shi ya tabbatar mini da cewa ba ta yarda da amsar dana bata bata
Yusi yana gefe a zaune ya yi nairainarai da ido saura kiris ya fashe da kuka dan tun jiyan nan dana mare shi bai zo wajan da nake ba. Kallo d'aya na yi masa na kawar da kaina daga kansa domin Ina so na horar dashi akan abinda ya aikata ko don gaba ya kiyaye furta abinda ba shikkenan ba.
Cikin sigar zolaya Babansu Fadila ya ce." Madam ba gaisuwa ne ko na yi wani lefin ne kuma."
Cike da jin nauyi na ce." Yi hakuri wallahi na d'auka dana fito na gaisheka, gabad'aya hankalina ne baya jikina."
Ya ce." Amma dai kya bari ki karya tukkuna sai ki tafi, da za ki bari ma akwai motar da zata tashi karfe goma sha daya na safe sai na kira direban yanzu."
Na ce." Anya kuwa zan bari ai ka barshi kawai zan iya shatar motar ma gabad'aya babu damuwa.
Cikin dai zolayar dai da ya saba da  sigar wasa ya ce." Au na manta Hajiya ce fa uwargidan a wurin Yallabai."

Murmushi kawai na yi na dubu anti Yagana tana tambayata yaushe zan dawo.'
Na ce." Nan da sati guda in sha Allahu zan dai kira ki idan zan taho din."
Ba ta ce komai ba ta fara tsiyaya kunun gyadar cikin wani madaidaicin fulas tana fad'in." Ki tafi dashi ko a mota sai ki kurba kina dai sauka ki kira ni."
Na ce." To shikkenan in sha Allahu......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram.Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan

saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*36*

Ta 'bata rai tana ce wa." Matsalata dake taurin kai Amina, kishiyarki wallahi ba a zaune suke ba, babban burinsu ki fice ki bar gidan, kin ga idan ba ki ba ni goyon baya ba sai na yi asarar kudina dubu arba'in na fitar aka ba ni turaran nan da kuma wannan rubutun."
Na cika da mamakin jin kudin da ta bayar har dubu arba'in lallai anti Yagana ta d'auki lamarin nan da girma, ai idan dan ta ni ce  wallahi ba wani yawon neman taimako da zan yi a ci kudina a banza. Na tabbata anti Yagana bata ta'ba zuwa wurin wani malami ba sai akan matsalata hakan ne ya sanya na amince zan yi amfani da maganin amma da sharad'in ko da bai kira ba to ba zata kira shi ba domin ta ce mini malamin ya ce idan bai kira ba to sai a kira shi.
 Ta amince da abinda na ce ni kuma na kar'bi rubutun da turaran a take a lokacin na fasa daya nasha ba tare da yakini ba.
Da kanta ta je ta hura wuta ta ruru sosai ta shigo da garwashin da yawa a cikin kasko irin na kasa ni dai kallonta kawai nake yi ina mamakin yadda ta d'auki al'amarin.
D'aki ta nufa da rushin wutar kafin ta kwalo mini kira na tashi na je na sameta tana kwance ledar turaran, ta ce." Sai kin cire kayan jikinki tsaf sai ki rufa da wannan zanin, amma idan kin zuba turaran akan wutar sai ki dinga yi kina kiran sunansa.
Fashewa na yi da dariya na fadi saman gado ina kyakyatawa domin duk yadda na kai ga son ganin na danne dariyar kasawa na yi.
Ta yi kasa'ke da ledar maganin a hannunta tana hararata. Ni kuwa Ina dariyar na ce." Wallahi anti Yagana dariya kike ba ni, wani irin turare ne wannan da har sai na yi tum'bur haihuwar uwata, na rantse da Allah malaman nan suna nema su jefa mata a masifa."
Ta sha kunu tana cewa." Kina d'auka abin nan da wasa ko Amina, nema ma ki ke yi ki mayar da ni mahaukaciya saboda baki da mutunci ko ina tsaye akanki amma ki sanya ni a gaba kina yi mini dariya ba za ki fahimci abinda nake nusasheki ba sai ranar da ma'kiya suka kai ki 'kasa tukkuna."
Ganin yadda ranta ya 'baci ya sanya na tashi zaune sosai na kar'bi ledar da turaran yake daure Ina fad'in." Zan yi yadda ki ke so anti Yagana"
Shiru ta yi mini tana cigaba da wurgo mini harara. Babu yadda na iya da ita haka na tashi na fara cire kayan jikina, ya rage daga ni sai rigar mama tana tsaye tana kallona na dubeta tare da cewa." Ko suma din na cire su?"
Ta girgiza kai." Ki bar su kawai ai."
Ban sake cewa komai ba na zuba turaran akan wutar lokaci guda hayakin mai kauri ya tashi na yi sauri na rufa zanin ajikina na dukufa kan wutar ita kuma da sauri ta kama hanyar fita tana fad'in." Kada ki manta ki dinga ambaton sunansa fa."
Na ce." To shikkenan."
Ina jin karar jan kofarta na cillar da zanin na tashi daga kan wutar na matsa gefe ina haki da tari ya sarke ni.
Hayakin ya cigaba da bin iska ina gefe guda. Na ji motsin bude kofarta a guje na d'auki zanin na je na dukufa kan wutar ta leko tana cewa." To kin ga haka

ai ya fi, kin shaki hayakin sosai, in sha Allahu da izinin Allah zai kira waya yau din nan sai a daidaita, malamin ma cewa ya yi hakuri zai bayar."
A zuciyata na ce.'' Anti Yagana da tun farko kin k'adaita Allah ba za ki nufi wajan wani malami ba, suma duk hasashe suke yi.
To haka muka yini muna tattauna sha'anin Hadiza da abinda ta aikata, ni ma yanzu na dawo daga rakiyar Ummansu domin ta zama bakin ganga na yarda itace take dorata a gwadabe mara kyau amma duk lokacin da zata kira ni a waya nuna mini take yi itama Hadizan tafi k'arfinta ha'kuri take da halinta a zahiri kenan amma a bad'ini bakinsu d'aya. Na riga na gama fahimtar cewa Hadiza da ni take gasa tun daga kan mutuwar aurena kawowa yanzu burinta itama ta tara arziki har ta kere mini.
Tun bayan sallar Isha'i na lura da anti Yagana jikinta ya yi sanyi duk wani abu da take yi babu kuzari domin abincin dare ma ni na yi mana towon samovita miyar ku'bewa tun yamma take ce mini jikinta yana ciwo dalilin da ya sanya kenan tasha Panadol ta kwanta amma dai karin kasalarta yana da ala'ka da dakon kiran wayar Alhaji Tajo domin yadda na fahimta ta gama aminta da abinda malaminta ya gaya mata.
Muna d'an ta'ba hira sama-sama Babandi ya zo, bai samu wata tar'ba ta arziki ba a wajan matar gidan anti Yagana kenan, ni kaina daurewa kawai na yi nake tanka masa amma duk da haka babu cikakkiyar sakewa kamar yadda muka saba,  ina jin hakan da ya fahimta ne ya sanya shi yi mana sallama ba tare da ya shirya tafiyar ba domin idan dai za mu had'u muka shafe sama da awa biyar muna hira ba tare da gajiya ba, yanzu kam ko minti talatin bai yi ba ya kama hanya ya tafi ba karsashi a tare dashi.
Anti Yagana ta rakashi da tsaki da harara duk ina kallonta ban ce mata komai ba.
goma da wani abu Babansu Fadila ya shigo ita lokacin ta shiga d'aki tana kintsawa.
Ya tsaya a falon muna dan ta'ba hira da yake akwai sabo a tsakanimu  dukda wani sa'in idan na zo garin har na kare kwanakina bai fi sau biyu muke had'uwa dalili shi din babban direba ne kuma yana da muk'ami a tashar da suke ajiye motocinsu da asuba yake fita sai dare yake dawowa kamar i yanzu.
Ya tsaya yana tsokanata da fad'in." Ranki ya dad'e ina kamun 'kafa fa, a cewa maigidan a irin wad'annan motocin nasa muna neman koda guda d'aya ce wadda za mu dinga lodi daga nan kudu, idan haya ake bayarwa a taimaka a ba mu, idan kuma za a ba mu ne sojan haya zuwa shekara biyu in sha Allahu sai mu mayar da kudin, dama tuntuni nake so na samu dama na bi ta karkashinki, kwanaki an ce mana ya rabawa direbobi biyar kuma uku daga ciki ma an ce kyauta ya basu ba mutum biyu ya kar'ba."

Tsakaninsa da Allah yake gaya mini babu wasa a cikin maganar. Ganin haka ya sanya ni ma na shiga nutsuwata na ce." Aikuwa ban san kana buk'ata ba wallahi tabbas watannin baya na ji yana maganar da wad'anda Allah Ya sa suna da rabo, amma in sha Allahu kuwa zan yi masa maganar idan na koma duk yadda muka yi  dashi sai na sanar da kai."

Da farinciki mai yawa ya fara godiya har da kirari kamar wani maroki na dinga dariya ina zolayarsa da cewa sharad'in idan na yi masa hanya ya samu babu shi ba kara aure fad'i yake yi." Na yarda ai tuntuni na gaya mini Yagana ta rufe kofar kece ba ki yarda ba."

Dariya kawai na yi domin nasan yana fad'a ne kawai amma ba har zuciya ba, babu wani namiji da zai so ya rayu ya mutu da mace daya yawancinsu suna ha'kura ne saboda wasu dalilai amma an riga an hallicesu da son mata wannan a jininsu yake akwai ma mazan da suke da tarangahuma sun yarda su tara matan duk abinda ma zai faru sai dai ya faru. To wad'annan sune za mu kira da masu rashin tsinkaye da hangen nesa.

Ki biyaa ni hakkina kafin ki karanta mini littafi yar uwa akwai hakkina akan ki domin littafin nan na kudi ne.

gajiya na yi da tunani na tashi na je na kwanta wanda bacci da k'yar ya d'auke ni. Misalin shida da rabi wayar Hamusu ta tashe ni daga b'ingirewar da na yi bayan sallar asubahi
Muka gaisa sosai dalili mun kwana biyu ba mu gaisa ba kamar yasan maigidan yana adawa da hakan a tsukin ya rage kira na a waya sai dai ya turo mini da voice note ta whasap. Ni ma sai na fi jin dadin hakan.  Nan yake gaya mini Gwaggo ce bata da lafiya dalilin da ya sanya ya kira ni domin jikin nata ya fara tsanani.
Cikin kankanin lokaci na ji hawaye ya cika kwarmin idona. Gabad'aya sai na diririce hankalina ya tashi sosai, na ce." Hamusu ina nan maiduguri na zo bikin yaran d'an'uwan Dada, ita Gwaggwon za ta san shi tunda tare suka taso. Amma zan yi kokarin d'auko hanya gobe yadda kake fad'in jikin nata hankalina ya tashi sosai wallahi, ina fatan kun kai ta asibiti.
 Ya ce." Kiran da na yi miki kenan, domin babban asibiti nake so mu kaita su bata gado sugar ne da hawan jini, mun je asibitin murtala likita ya dubata ya rubuto magani an Siya kwana biyu an samu sau'ki wallahi jiya kuma sai ta tashi bata iya motsa komai a jikinta, kuma ba damar na yi amfani da kudinki ban gaya miki ba "
Raina ne ya baci jin abinda yake fada. Na ce." Hamusu wannan wace irin magana ce, ashe akwai ranar da za ka iya nuna mini cewa Gwaggwo ba ta haife ni ba, kudin nawa wanene yake juya mini Ina ce kaine jigo har sai ka tambaye don za ka kai Gwaggwo asibiti wallahi baka taba ba ni haushi ba irin yau."
Ya ce." Ki yi hakuri anti Amina ta wani gefan fa Ina da gaskiya, kudi suna iya shiga tsakanin kowa shiyasa sanarwar take da amfani."
Na ce." Ka ga malam maganar ta isheni haka don Allah, ka je daga dubu daya zuwa dubu dari biyar har abinda ya yi sama na amince muddin akan gwaggo ne. Sai ya fara godiya ban jira na saurari sauran maganar ba na datse kiran na fita falo.
Anti Yagana tana kicin tana aikin karin kummalo Fadila tana taimaka mata
Yusi da sauran yaran sun fito bakin famfo suna ta burush da wasa da ruwa.

Na dan jingina a jikin bango a sanyaye na ce." Anti Yagana mun tashi lafiya ya hidima?"
Ta amsa hankalinta yana kan abinda take yi, na ce.'' Ina ganin gobe asubanci zan yi zuwa kano Gwaggo bata da lafiya yanzu nan Hamusu yake gaya mini jikin nata sai a hankali."
Ina dire maganar da take bakina Yusi ya zo ya tsaya da burush dinsa a hannuna.
Anti Yagana cikin alhini ta ce." Allah sarki Gwaggwo ciwon har ya kai ace bata san wanda yake kanta ba, kenan tana asibiti a kwance."
Na ce." Ina fa, tana gida saboda shashancin Hamsu bai gaya mini ba har sai da ciwon ya ci k'arfinta wai ya kaita asibitin murtala da farko yanzu kuma abin yayi tsanani shine fa ya kira ni yake gaya mini da abin haushi wai yana neman izini zai yi amfani da kudina.
Ta ja tsaki tana fad'in." Wauta da rashin hankali shikkenan don ya d'auki Gwaggwo ya kaita asibiti da kudinki sai ki ce masa don me, ya ba ni haushi wallahi."
" Wallahi ni ma ba ki ji yadda raina ya baci ba wannan ai shiririta ce rashin lafiya ya wuce komai, kuma ko dukiyata zata kare akan nemawa Gwaggwo lafiya anti Yagana wallahi ba zan damu ba"
Ya girgiza kai tana cewa." Kwarai kuwa ai Ido ba mudu ba ya san kima."
"Mama wai Gwaggo ce bata da lafiya?"
Na dube shi ya zuba mini ido da yanayi na damuwa a tare dashi.
Na ce." E, itace amma jikin da sauki alhamdulillahi."
A sanyaye ya ce." Mama idan za ki je zan biki don Allah....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*

*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*41*
"To menene Sahura ciwo fa aka ce, don na duba shi sai ya zama lefi, saboda kawai abin magana bashi da wahala, ke fa da bakinki ki ka ce yana buk'atar taimako, ni kuma ina so idona ya gane mini muddin akwai buk'atar taimako zan taimaka masa wallahi domin ni ma ya taimaka mini ya rike ni da yarana ko yaya ne dole na dubi alherin da ya yi mini a baya."
A dan sanyaye ta ce." Ban'ki ta taki ba sisi, amma kin san ba kowane namiji ne zai yarda da uzurinki ba, kin san kowa da irin fahimtarsa."
Tsaki na ja na ce." Sahura kyale ni don Allah, ba dai akan oganki kike magana ba, yanzu ma rigima muke yi sai mu d'ora da wannan."

"Wace irin rigima kuma sis, ba na son fa sharri mutumin nan na ji labari fa an ce goyaki ne kawai baya yi kuma ba ke ki ke yi masa ladabi shine yake yi miki, har cewa aka yi kin mallaka shi da mahaifiyarsa sai abinda ki ka ce musu a gidan."
Tana dariya ta kai k'arshen maganarta da zolaya.
"Sahura duk wanda ya gaya miki haka ya zalince ni wallahi domin kuwa ni kadai nasan da wanda nake zaune, ba zan iya 'boye miki abinda yake faruwa ba sis, amma wallahi kallon kitse kuke yi rogo, da yawa mutane za su dinga ganin ai kakata ta yanke sa'ka saboda mafiakasari mutane sun amince da cewa kudi sune jin dad'i alhalin ba haka ba ne,  na yarda da maganar nan da hausa ke fadi cewa ka auri mai zuciya ba mai dukiya ba, mutumin nan yana da tarin matsaloli wad'anda ya bi ya ninke abinsa ba wanda zai gansu sai wanda zama ya had'a mussaman ni dai da nake a matsayin matarsa. Akwai ci dasha kula da lafiya da biyan buk'ata ta aure duk akwai wannan to amma kin san wad'annan abubuwan da na zayyano miki idan babu kwanciyar hankali ba za su yi tasiri ba. Idan zan zaga kaf garin nan Ina sukar mutumin nan babu wanda zai yarda da maganata domin ya riga ya siye jama'a da alherinsa."
"Sis ki gaya mini abinda yake faruwa don wallahi ni gabad'aya kin kashe mini jiki, don Allah ki yi hakuri ki zauna a d'akinki."

Murmushi na yi Ina dubanta, itama magiya take yi mini na ha'kura na zauna ko bata fad'a ba na san dalilinta bai wuce irin na Anti Yagana ba.
Na ce." Sahura zaman bashi ne a wahala ba, abokin zaman shine matsala, ni idan ta ni ne wallahi ba ni da matsala dashi amma fa zan gaya miki abinda ba ki sani ba  ya sake ni akan wani abu da yake hasashe kuma bashi da hujja akai."
Cikin kad'uwa da tashin hankali ta furta." Saki kamar yaya k'awata, yanzu kina so ki gaya mini cewa babu aure a tsakaninku?"
"Ya sake ni shekaran jiya saboda yana zargina. Duk na kwashe abubuwan da suke faruwa na gaya mata. Jikinta ya yi bala'in mutuwa har da 'yar k'walla a kwarmin idonta ta ce." Wato ita dai 'ya mace rayuwarta ta kan kasance cikin 'kalubale akoyaushe duk abinda ta yi ba zata tsira ba, sis na ga dai harkar social media nan da ki ka yi neman na kanki ki ka yi baki taba aikata wani abin assha ba wanda zai zama tambari na zubewar mutuncinki. Kuma mutumin nan ba yaro ba ne a ganina bai kamata ace yana yi miki munanan zargi irin wannan ba, wallahi a wannan zamanin sis da wasu 'yan matan har gwara zawarawa ban ce duka 'yan matan lalatattu ba ne, amma wasu mazan na yanzu sun gane gwara su auri bazawarar sun san ita suka aura akan su kashe kudi wurin auran budurwa daga baya su gane ba kamila ba ce, kuma mata nawa manzon Allah s.a.w ya aura a matsayin bazawara, ko wannan ya kamata a ce wasu mazan na d'agawa mata kafa. Amma abinda na fi fahimta ga mutumin nan yana da zafin kishi wanda dama haka aka ce na maza ya fi na mata, kuma idan ya yun'kuro masa yakan iya kasa sarrafa kansa, amma ai kishi ba hauka ba ne, zai lalata auransa ne kawai bai sani ba, a wannan ga'bar gaskiya ba na tare dashi."
Na ce." To kin fahimce ni ashe,  Sahura a shirye nake akan wannan dalilin wallahi na tsinke auran nan, ban yi abu tunda kuruciya ba akan me yanzu zan yi, har wanda yake aurena ya gaza fahimtata, koyaushe addu'a nake yi Allah ya kare mu daga rudin zamani.  Shekaran jiya ya yi sakin jiya da safe ya ce ya mayar da ni. Ai aure ba abin wasa ba ne, ko 'yar tsana ba za a yi mata wannan wulakancin ba, Sahura dole ne na nuna masa nasan abinda nake yi."
" 'Kawata ina bayanki, amma don Allah kada ki zafafa da yawa nasan halinki, ki dubi shekaru da kuma matsayinsa da wad'anda suke k'asansa, dan fa kuskure ya yi kuskure gaskiya."
Na ce." Shi me yasa bai duba shekaru da matsayinsa ba, ai gudun zubewar mutunci yake yi a gari to idan bai yi wasa ba sabuwar jarida zata fita a kansa."
"A a 'kawata kada ki yi abinda duniya zata san me kuke ciki, ki sakaya auranku don Allah, shi dai sannu a hankali ki hukuntashi amma kada ki fitar da sirrinku, ai dan Adam tara yake bai cika goma ba, bai kyauta miki ba amma ki dubi abubuwan alherinsa a gareki ki rangwanta masa.
'Kwafa na yi tare da cewa." Mu bar maganar nan Sahura ta ishe ni wallahi, yanzu ashe yawo ake yi da ni a gari ana cewa juya shi nake yi, mutane basa tsoron Allah."

'Yar dariya ta yi tana fad'in." Wallahi cikin unguwarmu na ji maganar tana yawo, kuma daga gidanku ta fito Ummansu Hadiza ce take gayawa ma'kota ai kin shiga kin fita akansa da Mamansa  sai yadda ki ka yi dasu, Hadiza da ta zauna a gidan ta ga irin zaman da ku ke yi.

 "Ita Ummansu Hadiza tana d'auka yadda take bin malamai kowa ma haka yake, kin san mai yin abu sai ya dinga zaton wani ma yana yi, ai na gaya miki Sahura wallahi ban ta'ba tsugunawa agaban wani da zummar ya taimaka mini akan mutumin nan ba, kin fi kowa sanin halina. Anti Yagana ce ma da taga abin ya rincabe ta fara biye biye  na ce mata ba na so, duk abinda ya tunkaro bawa kawai ya nemi sau'ki a wajan Allah."
"Wannan shine gaskiya 'kawata domin babu wani abu da wani mahaluki zai yi maka face ya kara jefaka a masifa, kuma na ji labarin ma an ce Hadizan bata kasar wai ta tafi dubai saro kaya." Ta kare maganar tana dariya.
Na ce." Ni ma haka na ji Sahura na ce me Hadiza take so ta zama ne, ai mutumin nawa shi ta kira ya bata jarin kudi zaman da ta yi a wajena ta samu kofa a gabana ya ce mata duk lokacin da wata buk'ata ta tashi ta nemeshi. Wallahi Sahura ashe had'a baki suka yi da Ummansu suka shirya karya ciwo ga Fati wai tana da cancer za a yi mata aiki, duk suka daga mana hankali ni dashi a lokacin ya ba su miliyan shida ya kuma bata kofar tambayarsa duk abinda suke so shi ya d'auka da gaske ne sai da anti Yagana ta bincika ta tabbatar da cewa k'arya suke yi. Kuma maganar fa da nake yi miki lokacin da ya tura mata kudin zuwa Dubai din rikici muke yi don har ya yi sakin ma, bai gaya mini ba itama Hadizan ba ta gaya mini ba sai da Babanmu ya kira anti Yagana yana gaya mata.
Girgiza kanta ta yi  tare da cewa." Amina Hadiza 'yar uwarki ce, duk inda aka je aka dawo babu wanda ya isa ya raba tsakaninku tunda uba daya ba wasa ba ne, amma wallahi ki yi hankali da ita dan ta gurgud'e miki auren nan ba wani abu ba ne a wurinta, nasan ta fi ni kusanci dake amma kin san wani abu da ban gaya miki ba tun lokacin da abin nan ya faru da aka dinga yawo da sunanki a social media cewa kin ce ke ma a baki hakkin yaranki da Yallabai ya take, na dinga bibiyar lamarin wallahi har acct din da ya fitar da magana na dinga bibiya na kwafo lambar da aka bude acct din na ajiye, wallahi Koda na tsananta bincike akai sai na gano lambar Hadiza ce amma ba kowa ya san tana da ita ba, kuma yanzu ki shiga fece book ki yi sarcin din acct din za ki ga babu shi ta goge, dama ta bud'e ne domin ta 'bata ki."

Kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba. Littafin gudun aure na kudi ne.

Da mamaki mai yawa a tare da ni na ce." Anya kuwa Sahura Hadiza fa bata da wani boko  akanta ina ganin azancinta ba zai iya b'ata damar bude fece book ba har ta yi wannan rubutun."
"Itace fa na gaya miki, idan ba ta iya ba zata iya biyan kudi a bude mata ta yi amfani dashi a lokacin wanda ya bude mata ya goge shi gabad'aya."

Na ce." To idan na fahimta ta yi amfani da boyayyiyar lambata ne don kada a gane ita ce, tunda ai ina da lambata ko a fece book din ma ina ganin gilmarwarta."
"Shine ai abinda na gaya miki da wata wayar ta yi amfani amma da an tabbatar mini da cewa layinta ne kuma tana amfani dashi sa'i da lokaci."
Dariya na yi na ce." Lallai Hadiza abin har ya kai haka, to Allah Ya kyauta ke kuma Sahura sannuki da k'okari, na rantse miki da Allah ban ta'ba kawowa zuciyata ita ce ba."
Ta ce." Ke dai Allah Ya kyauta a wannan zamanin duk mutumin da Allah Ya rufawa asiri ai yana ganin hassada da bita da kulli na mutane."
Wayata na d'auka na duba lokaci sha biyu saura na ce." Sahura kinga sha biyu har ta kusa muna luguden lebe." Na kwalawa Salima kira dake can tana aiki, ta shigo na ce." Kawo mana shayin nasan kin gama dashi."
Ta ce." E Mama abincin ma na kusa."
Na ce." Sannunki diyar albarka ranar bikinki ban san wane shagali zamu sha ba."
Uwar ta fashe da dariya tana kallonta ta ce." 'Kugu za ki daure da gyalenki ki shiga filin rawa kawai Hajiya."
Ina dariya na ce." Sai kin fad'a ma, ai rawa zan yi hadda juyi."
Gabad'aya muka fashe da dariya. Yarinyar ta yi saurin fita tana sinne kai.
Ta dube ni tana cewa." Kin san fa wani yaro dan gidan yayar babanta yana nan yana naci a kanta wai ya kama don Allah kada a bawa kowa shine fa uban ya zo yana gaya mini na ce to guda nawa Yusuran take da har za a fara wannan maganar shekara sha hud'u fa kawai don an ganta da tsayi shi yasa ake bata girma."
Na ce.'' Ai girman 'ya mace ba wahala Sahura Kuma ta isa fa, ai tana da san girma, amma dai da Idiris zai d'auki shawarata da na ce masa kada ya yi mata auran nan na gaggawa ya bari ta samu koda diploma ce."
Ta ce." Ya bari kuwa, ai shi idan magana ta 'yan uwansa ce baya wasa da ita, ni ma nafiso ta dan yi karatu ko yaya ne zai taimaketa anan gaba."
Na ce." Gaskiya hakan zai fi dacewa." Wayata na d'auka na kira Hamusu yana d'agawa na ce." Kana asibitin ne....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
[12/29/2025, 10:50 AM] Aunty B: TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450

4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*

*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*42*
Ya ce." E, anti Amina jikin Gwaggon kam alhmdullhi."
Na ce." To haka ake so, ko za ka zo ka d'aukar muku abinci gashi nan Yusura ta kusa kammalawa kafin mu zo din."
Ya ce." Ai yanzu nan ma Baba Zulai kanwar Babanmu suka zo da abinci dama kullum tana zuwa sai dare take tafiya wani lokacin ma da safe kafin na je ta riga ni, tunda sun hana kwana."
Na ce." To shikkenan Hamusu ka gaishe mini da Gwaggon da ita inna Zulai din kafin mu k'araso."
"In sha Allahu rabbi anti." Yafad'a cikin kulawa da girmamawa.

To sai wajejan biyar na yamma muka gama shiri nida Sahura muka fito da zummar tafiya asibitin. Yusura na gidan anan muka barta dama tunda suka zo na cewa uwar ta bar mini ita ba jayayya ta ce dama ai taki ce.
Hijabi nasa har kasa na rufe fuskata da nikab saboda ba na so jama'a su gane ni.
Tare muka shiga shago da ita na gayawa yaran zan fita amma ba zan jima ba zan dawo, ita Kuma Yusura na ce mata ta rufe gidan daga ciki.
A daidaita sahu guda muka d'auka har asibitin Malam.
Muna d'an ta'ba hira na ce." Sahura duk abin nan da nake yi wallahi idan na tuna halin da Alhaji Muntari yake ciki sai na ji kasala ta kama ni, haka kawai nake tausayawa masa ki ba ni kwarin gwiwar taimakonsa tunda ke ki ka gaya mini yadda yanayin jikin nasa yake."

Ta ce." Sis kina da raguwar zuciya gaskiya, na taimaka miki ta wace siga kenan?"
"Idan mun shiga sai mu binciki asibitin bangaran maza ko Allah zai sa mu samu d'akin da yake sai na dubo shi."
"Kina da tabbacin yana asibitin har yanzu watanni uku fa na ce miki da suka wuce, wata'kila ma an sallameshi yanzu."
Na ce." Sai mu sanya rana ki raka ni na duba shi a gidansa, wallahi har yanzu ina tuna irin alherinsa akan Kamalu ya yi mini kokari sosai akan Yusi lokacin da ya aureni bai bambamta tsakaninsa da yaransa ba."
Ta ce." Kina cikin wannan rikicin sis, kada ki rikitowa kanki wani don Allah ki bar maganar nan, idan ki ka yi masa addu'a daga nan ma ya isa ai Allah ya ga zuciyarki."
"Babu abinda zai faru Sahura Ubangiji da zuciya yake amfani." Shiru ta yi tana girgiza kanta kamar buk'atata bata damu karbuwa ba a wurinta.
To muna shiga asibitin muka fara cin karo da motocinsa tunda komai nasa baya 'buya duk motocinsa akwai alama mai d'auke da ayyukansa na yau da gobe
Cikin faduwar gaba na ce." Kada dai mutumin nan ya sauka." Na d'auka a zuciyata nake maganar sai da na ji maganar Sahura tana fad'in." Shine ma ai kin san komai nasa a bayyane yake duk inda yake sai an gane, kuma tunda naga wannan  motacin na tabbatar yana cikin asibitin nan."
Na ce." Sahura kin ga irin abinda nake gaya miki ko? Matar nan fa mahaifiyar tsohon mijina ce amma ya yi ruwa da tsaki akan lamarinta ni ya hana ni ma aiwatar da komai, don girman Allah ki gaya mini ta yaya za a yarda da abinda zan fada a kansa."
Muna cigaba da tafiya  ta ce.'' Kin san kuma Yana da tausayi da zuciyar Imani fa, shiyasa ake ta yi masa sha'awar mulki domin ana yi masa kyakykyawan zato da wahala ya samu labari ko ya ga mai neman taimako bai taimaka masa ba, ya yi da jiki da aljihunsa wannan yana daya daga cikin kyawawan halayensa.

Shiru kawai na yi ban ce mata komai ba domin gabad'aya kaina ya kulle da al'amarin nan da yake faruwa.
Kiran da ya shigo wayata ya katse nazarin da nake yi. Hamusu ne, cikin nutsuwa na daga wayar nasa a kunnena. Sai da ya fara gaishe ni tukkuna ya furta." Kun shigo asibitin ne anti?"
A takaice na ce masa ." Eh, na dora da fadin wai kai baka gajiya da gaisuwa ne Hamusu Ina ce da safe mun gaisa haka ma d'azu dana kira ka sai da ka gaishe ni gaisuwa nawa za mu yi ne a rana."
Dariya ya fara yi kafin ya  ce." Ai babu lefi anti girmamawa ce, kin cancanci hakan ne." Humm kawai na ce Ina ko'karin kashe wayar ya ce.'' Yallabai ma bai jima da shigowa ba tare da su Yusi suka shigo."
Ban yi mamakin jin cewa suna tare ba domin akwai Sukairaju a tsakani. A takaice na furta." To babu lefi muna daf da shigowa ni da Sahura.''
Ban jira amsarsa ba na datse kiran.

Ni da Sahura babu wanda ya sake wata magana har muka isa d'akin da Gwaggo take kwance wanda 'yansanda biyu ke tsaye a bakin kofa.
Ko ba a fad'a ba nasan masu tsaronsa ne. Muka kàrasa wurin suka nemi su hana mu shiga wai sai ya fito tukkuna.
Kawai na tsaya ina kallonsu dan ban iya furta komai ba Sahura ce take ko'karin nuna musu wani abu Hamusu ne ya fito tare da wani likita suna magana.
Ganinmu da sauri ya ce." Yallabai ya haka kuma iyalinsa ce fa, ita kuma wannan kawarta ce."
Da sauri wanda yake tsaye a bakin kofar ya gyara yana sunkuyar da kansa ya ce." Madam sorry ban gane ki ba kasancewar kin rufe fuskarki, a yi hakuri." A nutse na ce." Babu komai." Na juya ina sauraran tattaunawar da suka yi da likitan yana fad'in tunda jikin ya yi sau'ki za a iya sallamarta gobe ko jibi ya dube ni yana kara yi mini bayanin yanayin jikin nata, da kulawar da ya kamata a dinga bata da kuma canjin abinci da sauransu.
Na ce." In sha Allahu za a kiyaye. Ya yi mana sallama cikin girmamawa da kulawa ba don mun kai ba sai don alfarmar wani wanda duniya ta d'aukaka shi.
Hamusu shi ya shige gaba kafin mu bi bayan shi ni da Sahura haka kawai sai na fara jin faduwar gaba kamar wadda ta tunkari ajalinta.
Gwaggo na zaune sosai a gefan gado Yusi yana kusa da ita da lemon zaki a hannunsa yana bare mata. Yayin da shi kuma yake hakimce a wata kujera dake d'akin wadda take kallon gadon da Gwaggo take zaune. Da alama hira suke yi yanayin da muka riskesu gabad'aya fuskokinsu sun nuna farinciki da murmushi.
Sukairaju da abokin tagwaitakarshi 'Dahuru dama su biyu ne masu take masa baya escort d'insa kenan suna tsaye a kansa.

Mu kula da hakkin wani komai kankantarsa. Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ba.

Sai gwiwata ta yi sanyi ganin yadda kaf hankalin Gwaggo yake kansa cikin kulawa suna magana shi ma ya bada hankalinsa kacokan gareta.
Muka yi sallama gabad'aya ina kallon Sahura ta nufi wurin da yake da azama. Ni kuwa da sauri na kawar da kaina na nufi Gwaggo da kulawa ina fad'in." Alhamdulillahi Gwaggo jiki ya yi sau'ki ma sha Allah."
Yadda na rungumeta itama haka ta rungume ni ta dora hannunta wanda yake da wadatar lafiya a bayana tana fad'in.'' Na ji sauki sosai Amina, na gode muku kwarai da gaske, yadda kuka yi mana Allah Ya sa ku ma yaranku su yi muku, Allah Ya yi albarka."
Na dan gyara na zauna gefanta har yanzu ina ri'ke da ita a jikina na ce."Babu komai Gwaggwo, ai na yi wa Hamusu fad'a a lokacin da yake gaya mini, na ce daka yanzu kada ya kara bari sai abu ya yi nisa tukkuna zai gaya mini, ban ji dad'in abinda ya yi ba ko kad'an."
Murmushi kawai ta yi bata ce komai ba.

Yusi da tun shigowarmu yake ta satar kallona Ina kallonsa yaron kamar yana shakkata a tsorace ya ce." Mama ina yini?"
Na dubi shi a tsanake na amsa da "Lafiya lau ya kake?"
Da dan murmushi ya ce." Ina nan lau Mama ."
Na harareshi da fad'in." Ai na ji labarin shegantakar da ka yi, za mu had'u ne."
Dariya ya yi yana sunkuyar da kainsa. Jikina ne gabad'aya ya mutu sakamakon idonsa da ya zuba mini, a jikina na jiki hakan a nutse na dubi wurin da yake muka had'a ido fuskarsa babu yabo babu fallasa yake ta kallona. Sahura ta iso wurin da muke da wani irin yanayi a tare da ita, ba ita kadai ba ma na lura duk wanda yake d'akin bai ji dadin abinda na yi ba, shi ma Hamusu duk ya yi tsumu-tsumu sai ya'ke ya ke yi.
Cikin nutsuwa na dube tare da cewa." Yallabai barka da yamma."
Bai yi nauwar amsawa ba ya ce." Barkanmu dai mun same ku lafiya."
Na amsa da "Lafiya lau." Da wahala dama ya nuna akwai 'baraka a tsakaninmu bai iya nunawa a bainar jama'a ba zan yi masa wannan shedar ya iya taku.
Bayan amsawarsa ma sai ya biyo ni da kyataccen murmushi. Na yi saurin dauke kaina gabana na cigaba da bugawa. Ni kaina na san Allah Ya jarrabe ni shi, domin ko Yaya Aminu karyar so nake yi masa. wannan mutumin ya riga da ya gama sace zuciyata. Inda Allah Ya taimaka ni ban ta'ba nuna masa tsananin so ballantana ya rike hakan a matsayin makamin da zai ya'ke ni.
Gyaran murya ya yi gabad'aya muka dubi wurin da yake. Ya tashi tsaye a nutse ya nufo inda muke hakan ya ba ni damar kare masa kallo, sai na ga ma ya kara ki'ba a cikin 'yan kwanakin nan da ba mu yi a tare ba.
Na janye idona daga kansa Ina tunanin wanda yake cikin matsala ne zai murmure irin haka, rayuwarsa kawai yake yi ta jin dad'i tunda ai ba ke kadai ba ce da wata kawai yana yaudarar mutane ne. Hasashen zuciyata ya zauna daram a cikin kwanyata na yarda fa wanda yake tattare da damuwa za a same shi a firgice shi kam ya murje ya kara haske abinsa.
Kai na ya tsaya kamshin da yake fita daga jikinsa ya tsananta sakamakon kusantuwarmu sai jikina ya fara neman ya mutu lamarin da nake ta dankwafewa yana yunkoro mini. Kamshin da ya riga ya kama jikinsa shi ma yana taka muhimmiyar rawa wurin galabaitar da ni.
Sunkuyar da kaina na yi tsigar jikina ta na motsawa. Ya fara magana da dattako kamar ya cika cikakken mara aibu.
"Zan tafi Gwaggwo Ina addu'a da fatan Allah Ya k'ara miki lafiya, in sha Allahu kuma gobe da kaina zan yi wa Hajja jagora domin ta zo ta duba jikin naki."
Cikin rawar murya Gwaggwo ta ce." To na gode sosai, Ubangiji Allah Ya saka maka da alheri, abinda ka yi mana Allah Ya ninka maka ranar lahira, Allah Ya sa wannan taimakon ya zama shine matakin shigarka aljanna, kamar dai yadda na gaya maka ga Amina nan ita da yaranta mun baka amana yadda ka dubi yaran nan kaima Allah Ya dubeka, ni dai idan ta ni ce na baka yaran nan gabad'aya Allah Ya tayaka ri'ko."

Ya ce." Na kuwa gode gwaggo, dama ai Yusuf nawa ne, na kar'ba har dashi Kamalun kuma zan ri'ke kamar ni na haifesu, ai ni ne da godiya Gwaggo."
Sai ta sanya hannu tana goge hawayen da ya fara zuba a kuncinta. Sahura na taya ta.
Ni kuwa gabad'aya jikina ya gama mutuwa ashe bana nan gwaggo ta kasafce mini yara. To idan kuma muka rabu fa, dama an ta'ba kyautar d'an mutum, ni kuwa da wace irin kalma ya yi amfani wurin janyo hankalinta irin haka.
Har ya fice da tawagarsa ban dawo hayyacina ba sai da na ji muryar Sahura tana cewa." Lallai baka da ta Ido Yusi bin sa za ka yi ba zaka zauna wurin Gwaggo ka yi mata kwana biyu ba."
Da saurin gaske na dubi bakin kofa wanda ya yi daidai da lokacin da yaron ya bude ya fita da sauri yana dariya."
Na dubeta da mamaki mai yawa a tare da ni. Duk sha'kuwata da Yusi yau ya nuna mini iyakata  sam baya son ma had'a ido da ni.
Sai kawai na ji 'kwalla ta ciko  idona, amma ban bari ta zuba ba na dinga mayar da ita ina jin Gwaggo na ta fad'in nagarta da mutuncinsa Sahura dama haka take so ta biye mata suna ta binkito abubuwan da yake aikatawa na bayan fage.
Na juya ina laluben Hamusu a d'akin shi ma baya nan, daga ni sai Sahura da Gwaggwo da alama tun lokacin da ya zo tafiya ya bi bayansa shi ma.
Gaskiya masu kudi da mulki suna jin dad'i sai ka ga babba da yaro kowa ya yi mubaya'a.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*

*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*43*
Shiyasa idan a ka yi katari da wanda bai san menene zamani ba sai ya fara d'agawa da izza daga lokacin da Allah ya kar'bi damar daga hannunsa sai ya gane Allah daya ne.
Ban iya sakin jikina da Gwaggo ba tun bayan tafiyarsa bakina ya mutu domin kuwa ban ga abinda zan ce mata ba, mafi yawancin hirar ita da Sahura suke yin ta. Muna zaune inna Zulai ta shigo, mu gaisa cikin mutunci har aka d'an ta'ba wasa da dariya tunda macace mai barkwanci..
Sai bayan isha'i Hamusu ya dawo yana fad'in can Danbattan ya bi su. Har yana gayawa Gwaggo sakon gaisuwar Hajja kafin ta zo.
Murmushi kawai na ke yi ina kallonsa cikin raina ina tunanin irin dambarwar da muka sha akansa har da su Allah Ya isa. Allah sarki shi kuwa sai rawar jiki yake yi saboda kyawun zuciya.
Muka yi sallama da Gwaggo da alkawarin zan sake shigowa gobe idan ba a sallameta ba amma ba da safe ba sai yamma, saboda ba na so na sake riskarsa tunda ya ce zai kawo Hajja kuma da safen.
Bakin titi muka fita muna jiran abin hawa Hamusu yana fad'in." Anti mutanan nan suna da karamci wallahi ashe Yallabai gada ya yi wurin mahaifiyarsa wallahi ba ki yadda ta karamma ni ba jin cewar ni kanin mahaifin Yusi ne, ta sanya aka kawo abinci da abin sha har da kyautar kudi dubu talatin fa."

Littafin gudun aure na kudi ne, kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Murmushi na yi na ce." Hamusu kenan." Ya ce." Wallahi anti Amina da gaske nake fa samun mutane masu dattako a irin wannan zamanin sai an tona, su dai Allah ya gama yi musu komai."
Sahura ta cafe maganar tana ce wa." Sai ma ka ga yadda yake wasa da dariya da ma'aikatansa abin zai baka mamaki wallahi, ai muna cikin alheri Hamusu na gaya maka idan zai shigo kano sau hamsin a shekara wallahi sai mun san ya shigo domin mu da muke aiki dashi a sassan reshen kamfanoninsanan yana yi mana alheri kwarai da gaske.
Ya ce." Ni ma sheda ne anti Sahura na ga alherinsa yau ."
Na ce." Sheda a ina Hamusu Yayanka Aminu mai ya tsira dashi?"

Suka dube ni da  wani irin yanayi.
Na ce." Kwarai kuwa, ko za ka iya nuna mini abinda Yaya Aminu ya tsira dashi kafin ya mutu. Sai wahala fa, amma shine kake so ka bugi kirji kace kaima shaida ne ko akansa ko Hamusu.."

A sanyaye da rashin karsashi Hamusu ya bi ni da kallo a lokacin dana gama maganata. Yadda na fahimta kawai ya yi shiru ne ba wai don bashi da abin fad'i ba. Sahura kam akan tun akan titin ta fara yi mini sababi, abu ne mai wahala kaga abinda zai tunzurata tana da mugun ha'kuri da d'auke kai, ko a makaranta ma bata da abokin fad'a kowa nata ne, ansha yin fad'a kace-kace da muguwar gaba a ajinmu amma sannu a hankali ita take shiga rigimar kuma ta sasanta. Na lura kuwa akan mutumin nan bata da hakuri  tunda wannan shine karo na biyu da ta bud'e mini wuta kamar 'yar cikinta. Na farko lokacin da na yi dogon rubutu akansa a fecenook, dukda a waya mukayi muyasar yawun na lura ranta ya yi mugun b'acin dalilin da ya sanya ma kenan na sauko har na nemeta da ta yi mini jagorar ganinsa. Sai wannan shine karo na biyu sam ta manta akan titi muke fad'i take yi a gaban kowa ma za ki iya fad'in haka Amina domin na lura hankalinki ragaggene, to bari ki ji wallahi kanki kike da'bawa wuka, karonku na farko ke dashi ba ki labari ba, ballantana yanzu da kike karkashinsa. ai duk mai hankali zai fahimci jawabin da ya yi cewa babu dole akan abinda yake yi ma'aikatansa ne, ihisani ne kawai a tsakani kuma ke da bakinki ki ka gaya mini akwai wanda ya ke shirya wannan zalinci, wallahi abin kunya ne a ji wannan maganar daga bakinki sis, domin  duniya ce zata zageki, ni kan haka gaskiya zan iya yin nesa dake tunda ba kya d'aukar ke shawarata"
Ta karaci bambaminta ban tanka mata ba. Hamusu ne dai yake ta tausarta na yi musu shiru ina ta ko'karin tsayar da abin hawa. Kawai na ga ta tsayar da wani ta yi shigewarta tana gaya masa ja'in zai kaita.
Na saki baki ina bin babur din da kallo har ya 'bace daga wurin.  Mamaki mai yawa ya rufe, ni dai a ganina ban ga abinda tayar da jijiyar wuya akan maganata ba. Murmushi kawai na yi  ina gyada kai lallai lamari ya baci tunda Sahura ta yi irin wannan fushin mun tawo tare kuma mun rabu da takaicin juna.
Hamusu ya tsayar mini da abin hawa. Na shiga na zauna ina dan nazarinsa shi kansa yanayinsa duk babu dadi ya nuna abinda ya faru ba yi masa sukari ba. Hannuna na daga masa  ina fad'in sai ka shigo. Direban ya ja da k'arfi muka bar wurin.
Tsaf na samu gidan Yusura ta gyara ko'ina, tana kwance a falo ita kadai shiru sai ta ba ni tausayi sosai ta kar'bi jakkar hannuna tana yi mini sannu da zuwa. Na zauna babu k'wari a jikina ta kawo mini ruwa na dan kurba kad'an sai da na d'an samu nutsuwa tukkuna  na tashi na dauro alwala tunda magriba a hanya ta yi mana, gashi ana kiran Isha'i.
Tare muka gabatar da sallar da ita  bayan mun idar na ce ta zuba abinci ta ci, domin ni gabad'aya cikina a cushe yake. Saboda kada kad'aicin ya yi mata yawa na bata wayata na ce ta shiga ta yi kallo. Na shige d'aki na kwanta da tunani a cikin k'wanyata.

Ina daga cikin d'akin a kwance na ji  an kira ni a waya kafin ma na yun'kura ta shigo d'akin tana fad'in." mama ana kira."
Wayar na kar'ba ta kama hanya ta fita. Hamusu ne na daga a nutse ina kiran sunansa ya gaishe ni kamar koyaushe na amsa sai ya dora da fadin ." Anti ba zan samu shigowa yanzu sai gobe in sha Allahu Ina fatan babu matsala ko?"
Murmushi na yi na ce." Babu komai Hamusu ko kaima fushin kake yi da ni ne irin na Sahura?"
"A a anti, ai duk abinda ki ke yi kina yi akan d'an'uwana ta yaya zan yi fushi dake amma kuma fa maganar anti Sahura akan hanya take anti Amina, Ina ganin zuwa yanzu ya kamata ace kin manta da abinda ya faru, idan an yi duba da irin tarin alheran mutumin nan, bai cancanci suka da zambo a wurinki ba."
Dariya kawai na yi domin ni kaina na san ba ni da hujja mai karfi da zan ri'ke domin kare kaina. Na ce." To na ji ai ba zan ki amfani da shawararka ba Hamusu zan kiyaye."
Sai ya saki muryarsa sosai yana fad'in." Na ji dadin hakan sosai Anti Allah Ya kara girma."
A hankali na amsa Ina dan murmushi wato dai ni a ko'ina  ba ni da sa'a, ba ni da magoya baya muddin akansa ne.
Sahura na fara nema a waya domin ba na so ta kwana da takaicina. Kiran duniya ta'ki daga mini waya.
Sai na tura mata text na ban ha'kuri har da yar zolaya. Amma ba ta yi maido mini da amsa ba.
Ban ha'kura ba na sake kira nan bata daga ba sai na rabu da ita zuwa gobe da safe nasan ta dan sauka.
Na kwalawa Yusura kira ta shigo na mik'a mata wayar tare da cewa." Je ki cigaba da kallonki."
Tagogin d'akin na bud'e dalilin zafin da na ji yana nasata. Dama tun can ban sanya fanka a d'akin ba sai ta tsaye na saya nake amfani da ita to tana can shago yara na amfani da ita dalilin da ya assasawa uwardakin zafi abun ya hadu da tasowar hadari. Bude tagogin da na yi ya sanya sauro shigowa dole ta sanya ni barin d'akin  bayan na yi wanka na samu riga ta shan iska mai hannun shimi na sanya amma ta sauko mini sosai sai dai ta matse mini jiki sai na sanya hijabi akai na fito falon na samu Yusura ta bingire bacci ya kwasheta ga waya tana yi da film din bahubali wanda Yusi ya matsa dole sai da aka tura mini a wayar anti Yagana yake wai yana son film din zai dinga gani.
Dole bacci ya kwasheta ga iskar fanka ga ta hadari yake tasowa ba ina jin dalilin da ya sanya ma kenan d'akin ya d'ume da mashahurin zafi.
Babban bargon da yake shimfid'e akan katifata na d'auko da matashin kai biyu na gyara mana shimfidar sosai sannan na tasheta ta je ta yi fitsari ta dawo ta kwanta .
Yadda hadari ya had'o sosai na gabas da irin walkiyar da ake yi da wahala idan ba a yi ruwa ba domin hadarin gabas ba kokwanto yana zubar da ruwa.

Na fita na gyara abinda zan gyara na leka shagon lokacin suna ta shirye shiryen tashi dan ma da yawa daga cikinsu gidajen iyayensu a unguwar suke wasu kuma a shagon suke kwana.
Kofar ciki na rufe sannan na rufe ta falon na nemi waje na kwanta lokacin ruwan ya fara sauka kad'an kad'an.  Sai Kuma na ji ana ta'ba kofar na tashi zaune da mamaki. Kira ya shigo wayata da take ajiye a gefena don ban kai ga kasheta ba tukkuna. Hamusu ne ya kira
Cike da mamaki na daga wayar na ji shi yana fad'in." Anti har kin rufe gidan kenan Yallabai na yi wa jagora muna tare  ki bud'e kofar.''
Da fargaba mai yawa a tare da ni na ce." Yallabai kuma?"
Da sauri ya furta." Eh anti ki yi hanzarin bude kofar ruwan ya fara karfi."
Na yun'kura na tashi tsaye gabana na dan bugawa na dubi  lokaci a wayata goma da minti arba'in, ban san me ya kawo mutumin nan wajena ba a irin wannan lokacin ko zuciyarsa ce ta raya masa ya yi mini zuwan bazata domin ya kurewa 'karyata ko ya tsira ni. Idan na'ki bude kofar nan na d'auri kaina hasashensa zai tabbatar a kaina wannan dalilin ya sanya na fita cikin ruwan da ya fara karfi na  bude kofar.
Sune tsaye shi da Hamusu biyu kacal bai zo da kowa ba. Ruwan har ya fara jikasu. Hamusu ganin na bud'e kofar bai ce mini komai ba da sauri ya shige shago suka rufo kofa.
Jikina babu kuzari na matsa masa hanya ya shiga na tsaya na rufe kofar kafin na biyo bayansa....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*

*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*44*
A rumfa na iske shi yana bin wajan da kallo. Na tsaya kawai ina kallonsa jikinsa na dan d'igar da ruwa rigar jikinsa duk ta kwanta sakamakon ruwan da ya ta'ba shi.
"Kin yi mamaki ko?"
Maganar da ta fara fitowa daga bakinsa kenan.
Na ce." Ban yi mamaki ba, ai hakan yana daya daga cikin halinka dana sani."
"Wannan yarinyar fa?" Yafad'a yana duban wurin da Yusura take kwance. Na kalleta baccinta take yi sosai na ce." Yarinyar Sahura ce."
Ya gyada kansa kafin ya furta." Ni a Ina za ki sauke ni, annabi ya ce ka girmama bakonka."
"Ai ba ka gaya mini za ka zo ba, za ka iya zuwa shago ka kwana da yarana domin nan ne masaukin baki a gidana."
Ya tsaya kawai yana kallona kafin ya yi dariya wadda har sautinta ya fita ya ce." Idan za su yarda na kwanta a cikinsu ni a wurina ba komai ba ne ai Aminatu."
Shiru na yi ban tanka masa ba. Sai ya dubi jikinsa da yake d'igar ruwa ya kalle ni." Mu je d'akin naki, ki ba ni aron zani na d'aura."
Na ce." Ai ban zo da wasu kaya da yawa ba gaskiya ba ni da zani sai siket."
"Zan sanya siket din, ke da ki ke lukuta ma ki ka sanya balle ni."
Ganin Yusura na motsi ya sanya da sauri na nufi dakin ya biyo bayana. Da sauri na tayar da katifar da take kwance na tsayar da ita sai kafet kawai a wurin.
Muka yi cirko-cirko muna duban junanku kamar shekararrun zakarun da suke matsananciyar gaba da junansu."
"Ba za ki girmama ni kamar yadda Annabi ya fad'a ba kenan."
Ya fadi hakan kafatanin hankalinsa a kaina.
Na ce." Ai ba ka kira ni ka sanar da ni zuwanka ba ballantana na baka masauki."
"To ke din a karkashin wa ki ke, ko ni kin gaya mini za ki zo nan?"
Shiru na yi ban tanka masa ba sai ya tunkaro wurin da nake tsaye ban ja da baya ba amma Ina cikin matsananciyar fargaba.

Gabad'aya ya danne ni da kirjinsa har sai da na fadi a kasan wajan. Ya fara fadin." Mu yi kokawa idan kin isa." Na yi shiru dai ina kallonsa gabana na cigaba da fad'uwa. Ganin ban biye masa ba sai ya tsuguna
yana fad'in." Ki ba ni abinda zan sakaye jikina na cire wannan jikakkun idan na kwanta ciwo kuma ke ce sanadi domin zan iya rantse miki na fi karfin shekara talatin rabon da ruwan sama ya dake ni."
Muryata na d'an rawa na ce." Wannan kuma abinda ya shafeka ne.
Sai ya tsirawa fuskata ido yana kallo, na kawar da kaina domin yanayin kallon da yake yi mini ya fara sa'bata.
Yun'kurin tashi na fara yi ya mayar da ni ya zaunar ." Ban zo gidanki domin ki wulakanta ni ba da zummar sasanci na zo, na yarda na yi lefi ki yi hakuri."
Har cikin zuciyata na ji dad'in karayarsa wanda da wahala a irin wannan zamani namiji  karabiti ya yi wa mace lefi ya bata ha'kuri ballantana irin nawa mijin.
Àmma ban nuna masa hucewata ba, na sake daure fuska tamau na furta." Amma kasan abinda ka ke yi mini kuskure ne?"
"Na sani, dalilin da ya sanya ma kenan na ji zan iya jure duk wani cin kashi da za ki yi mini, kuma ba na so kowa ya ji na sake ki, mussaman Hajja."
"Ai na gaya maka tun farko yadda ita ta kulla auran yana da kyau da ta san abinda yake faruwa, ni a wurina babu lefi don ta ji cewa igiya daya ta samu tangard'a."
"Ban amince ba, ba zai yiwu hakurin dana baki ya tafi a banza ba, na gaya mini wannan lamari ya zama sirri a tsakaninmu na yi miki alkawarin in sha Allahu hakan ba zata sake faruwa ba."
Na yi shiru ban ce komai ba. Sai ya riko hannuna a hankali." Kin yi alkawari ko?"
Kai na girgiza na ce." Ni fa mutum ce mai zuciya ya ba zan ji zafi da takaici ba a duk lokacin da wanda nake aure ya gaza fahimtata. Saboda kawai bai samu budurcina ba, ya aureni ina sana'a domin rufawa kaina asiri sai kawai saboda son zuciya da rashin adalci ya dinga yi mini mummunan kazafi."

D'akin ne ya yi shiru tun bayan ajiye maganata bai ce komai ba sai karar saukar ruwan sama da ake ta shekawa. Na dube shi a hankali sai na ga yana rawar d'ari alamun sanyi. Muka had'a ido. Ya ce." Ki ba ni abu na gaya miki ko so ki ke yi na cire na yi tsirara ne sanyi ya dame ni."
Na tashi na zuga akwati na d'auko masa  zani da wata irigar irin ta jikina na mik'a masa ya tashi ya fara kicikicin cire kayan da suke jikinsa har yanzu rawar sanyin yake yi.
Ya miko mini zanina yana fad'in." Ban san yadda zan yi na d'aura wannan ba, kar'bi abinki wannan ma ta isa. Na kar'ba ina me saurin dauke kaina gabana na bugawa ganin yadda girmansa ya fito sosai domin  bai  kare jikinsa ba ya cire wandonsa akan idonsa sai na kauce daga wajan da sauri na matsa can gefe tare da sunkuyar da kaina k'asa fargabar wani abu na fara yi.
Ya juyo yana kallona na dai sake kawar da kaina a karo na biyu rigar ta kwanta ajikinsa tunda me hade da cotton da robo ce har ilayau girman nasa yana nan a tsaye na san kuwa da wahala idan ba mu yi rigima ba.

Kulle kofar d'akin kararaf alamun zura sakata shi ya dawo da ni hayyacina ya rufe ya nufo ni a hankali cikin karamin sauti ya ce." Rigar ta yi mini kyau ko?"
Kawai na saki baki ina kallonsa, nasan ba shi da alkunya da kawaici a wannan fagen kunya kuwa gaba ya bata ba baya ba, zai iya cewa zai neme ni ga yarinyar mutane akwance a rumfa, bayan haka kuma zahirin gaskiya ni da shi din muna ficewa ne daga hayyacinmu idan muna wannan lamari ihu da nishi da surutai samfur-samfur ba irin wanda ba ma yi.

Wata wawar runguma ya yi mini wadda ban yi tsammaninta ba a lokacin da ya k'araso wajan da nake tsaye. Gabad'aya muka fad'i a wurin domin kafafuna sun yi sanyi kuma ban tsammaci hakan ba. Sosai ya makale ni a jikinsa yana fitar da wani irin numfashi tare da sansanar sassasan jikina. Ban yarda na kar'bi lamarin ba domin yin hakan a wurina kamar abin kunya ne, na farko har yanzu zuciyata ba ta gama aminta da nadamarsa ba, na biyu kuma ba zan ta'ba yarda wata mu'amula ta shiga tsakaninmu ba yarinyar mutane tana kwance a falo na tabbatar da cewa abinda za mu yi ni dashi sai ya tasheta har ta fahimci wani abu.
Wata'kila ya yi amfani da wannan damar ne domin a ganinsa zan janye abinda na kudira domin sanin wacece ni ta wannan fanin babu kara balle kawaici ni dashi din duk kanwar ja ce ballantana yanzu da muke cike da tsananin buk'atar juna ko bai fad'a ba nasan hakurinsa ne ya kare shiyasa ya canza wata dubarar.
Na tattara dukkanin karfina na 'ban'bare shi daga jikina, domin d'umin jikinsa da yadda yake ta 'bari bai dame ni ba don ban kawo cewa zazzabi ne ya kama shi ba.
Na tashi tsaye ina numfashi gabana na cigaba da buguwa domin ban san kuma abinda zai sake biyo baya ba tunda na fi kowa sanin halinsa.
Ganin ya silale ya kwanta a kasan kafet din ya yi male-male kamar matacce daga wajan da nake tsaye ina jin sautin nishinsa sai jikina ya dan yi sanyi fargaba ta dirar mini dama ya gaya mini ciwo zai iya kama shi dalilin dukan ruwan da ya jima jikinsa bai kar'ba ba.
Na dan matsa kusa dashi a hankali na ce." Tunda ruwan ya tsagaita kuma sha biyu ba ta cika ba ni dai ka tashi ka tafi."
Idonsa da suke lumshe ya bude ya dubeni a hankali ya furta." Ba ki da imani Amina, ban yi tunanin kiyayyar da ki ke yi mini takai haka ba na gode."

Littafin gudun aure na kudi ne, kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina b.

Ya mayar da idonsa ya rufe yana sake janyo numfashi sama-sama. Har yanzu bai fara ba ni tausayi ba don sai nake ganin kamar karya yake yi don ya samu kaina ne. Na dan sunkuya kusa da kansa nasa hannuna a wuyansa sai na ji mugun zafi na cire da sauri na dora a saman kansa nan ma ya d'auki zafi kwarai da gaske.

Daga nan na gazgata cewa ba karya yake yi ba. Na dube shi a kwance sanye da rigata kamar wani mara galihu, kamar ba wannan attajiri mutumin nan da duniya take yayin sa ba, kamar ba wannan dattijon mutumin nan da daruruwan jama'a ke ci da aha a karkashinsa ba, kamar ba shine wanda jami'an tsaro ke risina masa ba suke kuma tsaron lafiyarsa. Yau gashi a karamin gida takurarre kwance a kasan kafet a d'akin da babu fanka. Sai na fara dawowa nutsuwata domin zuciyata ta fara yi mini munana tunani akansa wai idan ya mutu daga ni sai a shi a cikin irin wannan yanayin wace amsa zan bawa jama'a da manema labarai.

Na sake rud'ewa a lokacin da na ga yana kokawa da sauro don sai cizonsa suke yi yana bugewa da hannunsa.

Da sauri na riko kansa na dora a cinyata na furta." Sannu ka ga zazzabi ne ya rufe ka, dan tashi na gyara maka katifar sai ka kwanta ka ji."

Ya dan motsa kad'an kafin a hankali ya ce." Ba na so, ai ina ganin lokacin da ki ka tayar da katifar saboda kada na kwanta, na gaya mini ai ni nasan dole sai na yi mura da ciwon kai."

Murya na rawa na ce." To ai ba ni nace ka zo ba balle kace na kira ka ruwan sama ya doke ka asalima ban san za ka zo ba, kuma da ka ga hadari ai sai ka ha'kura."

Shiru ya yi bai ce mini komai ba sai jan hanci yake yi alamun ya toshe!

Na buga na raya ya tashi na kwantar da katifar ya ki tashi. Gashi sauro sai cizonmu yake yi ni da shi dukda akwai haske a d'akin amma bai hana sauron tasiri ba ga sanyi irin na ruwan da aka shara yana ta surarowa.

Na ji hawaye na nema ya k'wace mini domin hankali ya kara tashi a lokacin da na ga jikin nasa baya sau'ki sai gaba yake yi. Ya tattare waje daya yana ta rawar jiki. Na fara kuka cikin damuwa da zullumi na cigaba da rarrashin ya tashi na shimfida katifar ina da zannuwa a cikin akwatina na lullube shi. Ya ce ba zai tashi ba ai da farko ya nemi na bashi zanin na'ki na bashi."

Na sauke kansa dake cinyata da sauri na bude akwati na d'auko zannuwana biyu na zo na rufa masa. Domin na tabbatar da cewa bayan ciwon kan da mura da yake yi a yanzu zai iya wayar gari da zazzabin cizon sauro mai tsanani tunda bai saba ba. Da kaina na dinga buge masa sauron da tafin hannuna wanda duk yasha jininsa. Ni ban damu ma da wanda yake cizona ba. Cikin hawaye da jan hanci na ce." Ko za ka je cikin motarka ka kwanta a ciki tunda nan da sauro."

Cikin halin da yake ciki ya ce.'' Har yanzu dai ba ki yi maraba da ziyarar da na kawo miki ba ko, ki ka sani ma ko mutuwa zan yi sallama na zo yi miki."

Na sake shiga tashin hankali jin abinda ya furta. Ba shakka a wannan lokacin ana tsaka da yin mutuwar fuj'an, don an ce maka mutum ya rasu babu jinya kada ka yi mamaki.

Na karaya sosai da sosai cikin kukan da nake ta dannewa na ce." Ba zaka mutu a gidana ba, wane hali kake so na shiga wasu cewa za su ni ce na kashe ka."

Ya yi shiru bai ce komai ba. Na cigaba da kuka a hankali don ba na so dalilin abinda yake faruwa Yusura ta tashi. Kansa da yake cinyata nake ta shafawa ina ta jijjigashi domin na rasa ma abinda zan yi, ba na ajiyar magani balle na

bashi gashi an yi ruwa dare ya tsala ba na tsammanin za a samu masu chamis.
Agogon da yake d'akin na duba sha biyu da arba'in, ruwan ya d'auke tsaf. A hankali na sauke kansa na janyo zannuwan na rufe shi gabad'aya har fuskarsa na tashi zan fita. Na ji ya ce." Ina za ki je?"
Da sauri na ce." Zan duba shago ne idan ba su kwanta ba sai na ce Hamusu ya duba chamis mafi kusa a samo maka magani.
Ya ce." Dawo a bari sai gari ya waye abu daya za ki yi mini na samu bacci."
Na dawo na zauna ina fad'in." Menene?
Ya tashi zaune yana kallona muka zubawa juna ido da gaske ciwo yake domin alamun hakan ya bayyana a fuskarsa.
Ya furta." Ni ban iya mura fa ba, tana galabaitar da ni sosai, ki shimfidar da katifar."
Ban ce komai ba na tashi na yi abinda ya bukata domin ni a wannan ga'bar kokarina kawai na samu bacci ya d'auke shi da safe koma menene sai ya faru.
Ya dube ni a hankali ya ce." Cire hijabin ki kwanta."
Wallahi sai a sannan na tuna da karamin hijabi a wuyana."
Na cire na kwanta kamar dai yadda ya buk'ata, na zuba masa ido ina jiran ganin abinda zai yi a gaba. Ya hayo katifar da zannuwan dana rufe shi kawai naga ya kwanta a saman jikina ya fara gyara zannuwan domin lullube mu.
Jikina ya d'auki zafi sakamakon zafin da jikinsa yake yi, shiru kawai na yi ban ce masa uffan amma shi kansa ya san ba zan iya daukarsa a haka har garin Allah ya waye ba kamar akwai zalinci a ciki.
Cikin d'an karamin sauti a daidai fuskata na ji hucin numfashinsa Yana fad'in.
" Zan d'an fi jin sau'kin sanyin da yake damuna, idan kin gaji sai ki maye gurbina."
Cikin d'an jan numfashi na ce." Ban gane na maye gurbinka ba, amma kai ma kasan hakan ba zai yiwu ba ko kana fa da nauyi.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550

5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*

*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*45*
"Duk nauyina ai ban kai ki ba, na ce idan kin gaji ki dawo samana shikkenan ko?"
Shiru na yi. Muka cigaba da sakin numfashi jikinsa ya fara shikawa alamun bacci ya fara d'aukarsa. Daga zarar na motsa zai motsa shima. Na furta." Gaskiya sai dai ni na maye gurbinka da kyar fa nake numfashi wallahi ka fi ni nauyi."
Bai ce komai ba ya Birkita ya kwanta kan katifar yana fad'in." Hau shikkenan ko?'
Na gyara zannuwan na hau yasa hannuwansa biyu ya tallefeni na lullube mana jiki da zannuwan amma basu ratsa mu duka ba.

Cikin hukuncin Allah kuwa bacci mai nauyi ya kwashe shi. A hankali na zame jikina na dan kwanta a gefansa Ina kallonsa yana sauke numfashi mai tafe da sarkewa daga kirjinsa ya yi. Har yanzu ina jin d'umin jikinsa a jikina da gaske zazzabi da mura ne suka kama shi da gaske.
Zannuwan na gyara sosai ya rufe har kafafunsa amma ban da fuskarsa saboda fitar numfashi.
Na yi amfani da wani karamin mafici na roba Ina dan kore masa sauron da yake ta zarya a d'akin.
idona biyu asuba ta yi. Masallatai ana ta kiraye kirayen sallah.
Na tashi zaune a hankali ina dubansa lokacin ya motsa da wani irin tari wanda yake nuna alamun k'irjinsa a cushe yake da majina.
Cike da zullumi cikin zuciyata na kama salati domin ni a ganina wannan dan dukan ruwan bai kai ace ya lafke irin haka ba.
Ya tashi zaune yana cigaba da tarin na zuba masa ido har ya lafa a hankali na furta."Sannu."

Ya amsa can kasa kafin ya ce." Ya zan yi na yi sallah ne, ni kaina na fara nadamar zuwa gidan nan naki Amina."
Na dubi rijar jikinsa duk ya yi wata kala ya firgice na dan ji tausayinsa kad'an domin da gaske baya jin dadin jikinsa.
Na ce." Ni ban san yadda za ka yi ba. Ga kayanka nan duk sun jike har gajeran wandon da singilitin."
Ya yi shiru yana dubana kafin ya furta "Zan yi sallah a haka ai akwai uzuri ki zuba mini ruwa." Ban ce komai ba na tashi na shiga bandakin da yake jikin d'akin na zuba masa ruwa a buta Na fito lokacin har ya sauko daga katifar na bashi hanya ya shige bandakin.
Dadduma na shimfida masa na jira shi ya fito tukkuna ni ma na shiga na dauro alwalar....
Koda ya idar da sallar katifar ya koma ya kwanta bai ce mini komai ba a wannan karon tarin shi yafi matsa masa.
Ni ma ban ce dashi komai ba na kwashi kayansa na fita dasu. Na samu Yusura tana motsi na dan bubbigi kafarta ta tashi da sauri na ce." Taso ki yi alwala."
Na fita tsakar gidan da kayan a hannuna wanke su na yi tas na shanya cikin ikon Allah rana ta fito mai haske sai na mayar da kayan idonta  domin su yi saurin bushewa.
Yusura ta fito tana fad'in." Mommy ina kwana mun yi baki ne?"
A takaice na bata amsa da cewa." E jiya kina bacci ba."
Ba ta sake cewa komai ba ta nufi kicin tana cewa." Dame zan fara mama"
Na ce." Ki dora ruwan shayi  ki sanya kayan kamshi sosai ki dan sanya barkono a ciki ko uku ne."
Ta amsa da sauri kafin ta bude kicin din ta shiga.
Na sake komawa d'akin na kwashe takalmansa na shige masa dasu ciki. Na dube shi  har yanzu bacci yake yi lakadan.
Wayata na d'auka na fito falon na nemi Hamusu yana d'agawa na ce." Ka tafi asibitin ne baka shigo mun gaisa ba."
Da sauri ya ce." Haba dai anti na ce bari na dan jira gari ya kara yin haske sai na shigo mu gaisa kafin na wuce ko kina bukatar wani abu ne.
Na ce." Sosai kuwa wai d'an dukan da ruwa ya yi muku jiya fa Yallabai na kwance kashir'bar mura da zazzabi har da tari sun kwantar dashi."
Cike da damuwa ya furta." Subahanallahi! ai anti shiyasa nake ta ce miki ki bude kofar kin san akwai yanayi na girma da shekaru bayan haka kuma jikin bai saba ba, ni kin ga lami lafiya na kwana kuma na tashi garau da ni, ba na jin wani sauyi.
"Hakane yanzu nan babu wani chamis da suka bude tunda yanzu gari ya waye kana da abun hawa ka je can asibitin wurin masu sayar da magunguña ka samo masa maganin mura da tari amma mai kyau."
Da sauri ya furta." Anti ba ma sai na je har can ba Ina fita babban titi zan samu."
Na ce." Shikkenan sai ka dawo.'' Shi ya riga ni kashe wayar kafin na ce me na ji tashin karar babur d'insa Hamusu kenan.

D'akin na koma ina jin Yusura na ta aikace aikace sosai yarinyar ta horu da aiki gashi nan babu abinda ba ta iya ba na rayuwa.
Ido a bud'e na same shi yana numfashi da baki. gabana ya bada wani irin sauti rass!  yadda ya tsayar da idanuwansa a saman rufin dakin sai naga kamar wanda ba a jima da zare masa rai ba.
A sukwane na nufe shi kafafuna na kyarma. duban da ya yi mini shi ya dan sassauta fargabata. Na zauna kusa dashi ina fad'in ." Ka tashi ga tea na dafa maka mai kayan kamshi zai taimaka maka sosai muryarka ta bude yanzu Hamusu zai kawo magani sai kasha, amma ni ba na tsammanin wannan dukan ruwan ne ya haddasa maka wannan murar  saboda ka fa yi tafiyar mota."
"A jirgi na zo ni malama." Ya fad'a yana lumshe idonsa. Na ce.'' Na sani amma ai ka ninka dambatta sau biyu wannan iskar daka sha'ka ta isa sanya maka lalurara.
"Ke a tunaninki a wace irin mota nake irin wannan tafiyar?"
Shiru na yi ina nazari. Gaskiya ne a irin motocinsa babu wata kafa da iska zata shiga har ta janyo masa toshewar hanci manyan motoci ne masu tsaro.
Ya furta." Ko kin so ko kin ki kece sila, ni ai ban zo da niyyar kwana ba ruwan da ya ritsa dani ne, kuma na gaya miki sulhu na zo wurinki ba wani abu ba."
"Ai sulhu ya k'are tsakaninmu na gaya maka ba zan koma can ba gaskiya abinda yake zuciyata kenan."
Na fad'a tare da kawar da kaina gefe.
Ya nisa kafin ya ce." Na ji amma kin san kema ba ki da hujjar da za ki ce sai a nan za ki zauna ko ba zai yiwu ba, muddin na amince miki akan bukatarki dole ni ma ki bi ra'ayina ki zabi daya daga cikin gidajen da nake da su anan ki zauna."
"Menene da nan din?"
Bai kai ga magana ba attishawa ta tare shi ya dinga yi har sai da na tashi na nemo masa tissue ya dinga fyace majinar data tsinke. Ya tara tissue din a wuri d'aya na kwashe na je na zuba ashara na dawo na same shi har yanzu yana ta attishawar dai.

Kada ki karanta littafin nan ba tare da kin biya ni hakkina ba. Littafin gudun aure na kudi ne.

Lallai a yau na sake tabbatar da cewa mura tana daya daga cikin manyan laluran da suke galabaitar da jikin dan adam, daga jiya zuwa yau gabad'aya kamminsa sun canza fuskarsa har ta dan kumbura ga dukkan alamu ma dai yana da matsalar sanyi a jikinsa shiyasa da aka motsa shi ya tashi gabad'aya.
Fita na sake yi daga d'akin na samu Yusura tana soya indomi da kwai na ce ta miko mini fulas din shayin da yake gefanta ta had'o mini da kofuna biyu masu dan girma na gilas.
Na sake komawa d'akin yana kashingide attishawar ta lafa.
Ya bi ni da kallo a lokacin da na kàrasa wurin da yake har na tsiyaya masa shayin da yake ta tiriri da k'amshin kayan shayi bai d'auke idonsa daga kaina

ba. Ni ma ban ce masa komai ba na fara motsa masa shayin har sai da ya yi daidai yadda zai yi dadi sha. Na mika masa babu jayayya ya kar'ba har da godiya.
Gefe na zauna ina d'an sauke ajiyar zuciya. Na ji yana cewa." Har yanzu ban gayawa Hajja kina garin nan ba, haka zalika ma na gargadi Yusuf akan kada ya sanar mata Ina so ni dake mu gama magana yanzu da daddare na d'auke ki a mota domin ki duba gidan da za ki zauna."
Ba tare da na kalleshi ba na ce.'' Wai me yasa ba ka so Hajja ta san abinda ya shafe mu ne, kada fa ka manta mahaifiyarka ce, baka da hurumin boye mata abinda yake faruwa da rayuwarka."
"Wannan ai ba abin alheri ba ne shiyasa nake lullube mata."
Na ce.'' Yanzu ka amince kana kuskure ko?"
Ya d'aga mini kai alamar E.
Girgiza kaina kawai na yi ban kuma yi mamakinsa ba domin duk abinda yake yi mini a yanzu yana yi domin ya samu kaina, shiyasa duk abinda na ce ya yi kai tsaye yake amsawa babu ja'inja, a ganina kuma hakan ba zai hana shi watarana idan na ha'kura ya sake kuntuka mini ba."
"Na ji dadin shayin nan sosai na gode miki."
Maganarsa ta dawo ni da hayyacina. Na dube shi sai na ga yana kallona shima kafin a hankali ya ce." Kin kasa samun nutsuwa ballantana ni ma na samu nutsuwar da zamu cigaba da gudanar da rayuwarmu, akwai abinda nake so na gaya miki wanda ya shafe mu ne gabad'aya da duk wani makusancina amma ina fargabar ki juya mini magana ko ki ji kamar da gayya na gaya miki."
A tsanake na ce." Ni babu irin wannan gilin a zuciyata me zai sanya ka sanar da ni alheri kuma na ji b'akinciki idan ba ka sanya ni daya daga cikin masoyanka ba to na tabbatar zan zo a ta biyu don haka ina yi maka fatan alheri akan duk abinda ya sami rayuwarka."
"Na gode sosai, Allah Ya yi miki albarka."
D'akin ya yi shiru ni ina ta jiran na ji ya gaya mini abin alheri ya yi shiru yana ta kurbar shayin yana lumshe ido  da gaske ya yi masa dadi. Na ce.'' Idan bai isheka ba akwai sai na tsiyaya maka."
"A a, ya isa wannan din an jima dai kafin na tafi zan kara shan wani."
Na kar'bi kofin daga hannunsa na ajiye  sai na ji ya ce." Kin cire key din motata cikin aljihun rigata ko?"
Ban ce komai na janyo handbag d'ita na d'auko masa mukkulin .
"Ina Hamusu ba shi ya bude motar ya debo mini wayoyinsa.
Rufe bakinsa ke da wuya Hamusu ya shigo gidan na tashi da sauri na fita na same shi suna magana da Yusura hannunsa ri'ke da ledar magungunan na kar'ba tare da mika masa key din motar na ce." Yallabai ya ce ka debo masa wayoyinsa a mota."
Ya kar'ba ya fita da sauri
Allah Ya sa jiya da ya yi mini sayayya ya sayo rowan roba swan na d'auki daya na sake komawa d'akin.
Na ce." Ga magunguñan  wayoyin kuma yanzu zai kawo."

Ya kar'bi ruwan da maganin Ina daga tsaye duk Ina kallonsa ya 'balli maganin ya sha.  Na ce." Ko na dan dafa maka wani abu mai dan nauyi kafin ka tashi nasan maganin mura da kashe jiki wata'kila ma bacci ya d'auke ka yanzu."
Ya ce." Da kuwa kin kyauta amma towo na garin dawa, miyar kuka kuma."
Na ji shigowar Hamusu a karo na biyu muryarsa  a falo yana fad'in." Anti ga wayoyin." Fita na yi da sauri na amso masa shi kuma ya juya  zai fita na ce." Akwai abin kari Yusura ta yi Hamusu ka zauna ka karya zata had'a maka komai sannan don Allah idan ka shiga cikin gari ka hado mini kayan towon dawa."
Ya ce." In sha Allahu anti."
K'aramar wayar a kashe take babbar ce a kunne na mik'a masa ya kar'ba cikin nutsuwa ya fara dubawa, ganin haka sai na juya zan fita hankalinsa na kan wayar ya ce." Ina za ki je kuma ke da ki ke jinya."
Dawowa na yi na zauna  ban ce komai ba.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

 https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
  *Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*

*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen  gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari  ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har  Madiga  tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma,  dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce  dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*

*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye* +2348032089456

*46*
Ya d'an duba abinda zai duba kafin ya dube ni a nutse ba tare da nuna nishad'i ba ban dai sani ba ko b'oyewa ya yi ya furta." Kin san da cewa Hauwa tana da juna biyu?"
Gabana ne ya buga da karfi sakamakon jin maganar da ta yi tsalle ta fito daga bakinsa ban kuma tsammaceta anan kusa ba.
Sai da na yi namijin ko'karin daidaita kaina don gudun kada ya gane kid'imewata na kar'bi maganar da ya dumfare ni da ita da annashuwar da ban shirya yinta ba na ce." Kai ma sha Allah ko shine dama abinda ka ke cewa za ka gaya mini?"
Ya gyada kansa da kwarin gwiwa ya furta." Kwarai kuwa na so na gaya miki tun kwanakin da suka shige to ban san yadda za ki ji a ranki ba, sai kuma wannan rikicin ya b'alle a tsakanimu zan fi so ki samu nutsuwa mu daidaita a tsakaninmu ke ma ki samu na ki cikin zan ji dad'i na ga kuna yi mini jereran haihuwa."
Na danne abinda yake yun'kuro mini na tsantsar kishi da tausayin kaina na furta." Na taya ku murna sosai, Ubangiji Allah Ya raba lafiya ya kuma raya abinda za a samu. Maganar na samu ciki na haihu ina ga abu ne mai wahala domin ba abin wasa ba ne d'aukar ciki da rainonsa balle a zo kan k'adami na haihuwa. Tunda har jininmu bai hadu ba ina ganin mu ha'kura kawai da haihuwar nan Yallabai ai kai baka da matsala ni ce ma abin tausayi."
Na kare maganata idona a tsakiyar nasa idon.

"Ina ce wannan maganar mun rufe babinta tun wattanin da suka gabata dalilin da ya sanya fa kenan nake jin shakkun gaya miki saboda na fi kowa sanin halin rigimarki."
Na ce." Me ka mayar da ni mara son zaman lafiya ko me? ko duk wannan addu'ar da fatan  alherin da na yi muku baka gamsu ba har sai ka jefe mini magana idan ka boye mini cikin matarka ai ba zaka 'boye mini haihuwar ba tunda ba zata ta'ba dawwama dashi a jikinta ba."
Shiru ya yi mini bai tanka mini ba.
Hakan ya kara dagula mini raina. Gabad'aya ma sai nake ganin yana so ne ya raina mini wayo ne ya muna tsaka da rikici ya wulakanta ni har da tukwicin saki ban yi masa komai ba kuma ya zo ya ce mini na taya shi murna akan wane dalili. Haushinsa da nake ji sai ya dawo sabo dal, na ji kamar na ce ya bar mini gidana  amma babu halin hakan.
Ya kwanta tare da rufe idonsa yana jina ina ta sakin maganganu bai tanka mini ba. Na goge hawayen da ya d'an zubo mini a kumatu na tashi na fita.
Hauwa tana da ciki wannan ya nuna cewa daga zarar ta fara haihuwa zata kar'bi gidan. Ni kuma saboda son zuciyarsa na d'auki ciki na yi wahalar

rainonsa da nakud'a na haihu daga baya abinda na haifa ya mutu. Ita Hauwa itace mai rayayyun 'ya'ya kenan.
Kishi ya rufe mini ido gabad'aya tunanina ya kulle har sai da muka yi waya da Anti Yagana ta sake mayar da ni hanya tukkuna na dan samu sasaauci tabbas Allah ne mai yi kuma shi ne mai kashewa da rayawa.  Idan ya so duka yaran da Hauwa zata haifa su zama rayayyu idan ya so kuma ya d'auki ransu ba kuma tare da wata lalura ba. Tabbas akwai wannan ciwon kuma kisa yake yi bayan ya gama galabaitarwa amma hakan ba zai zama hujjar da za a ce ba za a haihu ba domin yana iya canza komai hakan ba abu ne mai wahala ba a wurinsa. Da wannan tauhidin nata muka yi sallama jikina duka babu karsashi da sukuni na sake yin tubus a lokacin da na tuna irin rantsuwar da ta dinga yi akan yadda ta tabbatar da cewa yana sona domin idan babu soyayya ba zai ta'ba zama irin yadda nake so ba har ya kwana a k'ukutance gida irin wannan da babu tsaro a cikinsa.
Haka na wanzu cikin nazari da tunanin rayuwar da zan fuskanta a gaba.
Dutsan guga na ce Yusura ta kar'bo mini a shago, tunda ko babu wuta babban gen suke kunnawa da kaina na goge masa kayan tsaf na ajiye masa a gefansa bacci yake yi sosai wanda na tabbatar da cewa maganin da ya sha ne yake tasiri a jikinsa.
Ni da yarinyar dai muka yi akin towon har da man shanu ya sayo na kuwa soya shi da albasa mai yawa. Na ce idan zai tafi asibiti sai ya zo ya tafi dana Gwaggo domin zai yi mata dad'i a baki.
Na had'a masa komai cikin babban tire har zobo na yi masa wanda ya ji citta duk don saboda ya samu sau'kin kirjinsa.
Biyu saura na koma d'akin har yanzu dai bai motsa ba ga lokacin sallah.
A hankali na dan bubbigi gefan katifar bashi da nauyin bacci dama can ya bude ido yana kallona na ce." Lokacin sallah ya yi.".
Ya yun'kura ya tashi zaune yana fad'in." Ina buk'atar ruwan zafi wanka zan yi tukkuna."
Na ce." Da ka ha'kura da wankan nan tunda ba ka jin dadin jikinka."
Girgiza kansa ya yi. "A a ki sama mini ruwan d'umi kawai.
Na tashi na fita ban sake cewa komai ba. A babbar tunkuya na d'ora masa ruwan sai da ya tafasa tukkuna na juye a bokiti na surka da d'umi sosai na kai masa bandakin d'akin.
Ya tashi jikinsa da kwari sosai ya shiga bandaki na bi shi da kallo jikina a d'an sanyaye ni kuma shine kaddarata jiyyarsa tsakanin  jiya da daddare  da yau jikina ya nuna ya na yi muguwar gajiya saboda kai kawo.
Maganarsa na ji daga bandakin wai na mika masa kayansa.
Ya zuro hannunsa na bashi kayan gabad'aya har singilitin da wandon ciki.

Kada ki karanta wannan littafin ba tare da kin biya ni hakkina ba. Gudun aure na kudi ne

Na je na d'auko tiren dana shirya masa abinci na ajiye masa a gefan daddumar dana shimfida masa.

Bandakin tsakargida na yi wanka na koma cikin d'akin na same shi ya idar da sallah yana waya da Hajja har yana cewa da ita ta bashi Yusi. Ban ce komai na fara had'a masa abincin a maidaidaicin filat na ajiye a gabansa gefe da yajin daddawa da man shanu.
Na tsiyaya masa zobon a kofi.
Ga mamakina na ji ya fara dariya harda kyakyatawa ina jiyo muryar Yusi kad'an-kad'an ko me yake ce masa oho, na ji yana fad'in." Idan na kasa juyo da hankalinta kai ma sai ka zo ka gwada taka sa'ar don wannan Maman naka ta fini rigima."
Na ji maganarsa Yana fad'in." Dukana za ta yi wallahi ni tsoronta nake ji Baba."
Yana dai dariyar ya ce masa "idan ta dake ka sai na rama maka ai."
Jin haka na san da ni suke lallai ma Yusi ashe na  zama abin zolaya a wurinsa, ban yi tsammanin akwai ranar da za ta zo yaron nan ya manta da ni ba.
Suna gama wayar ya dube ni yana fad'in." Kin ji ni da Yusuf ko? shi ya ba ni shawara na zo na baki hakuri, da na ce ya zo mu je tare ya ce a a dukansa ki ke yi.''
Murmushin takaici na yi na ce." Ai na ji abinda kuka shirya kai kuma ka rasa wanda zai baka shawara sai wannan mashiriricin."
Ya d'an janyo filat din da  nasa masa towon ya tallafe da hannunsa yana fad'in." To menene ai yaronki ne ya rayu dake zai fiye da ni zai fi kowa sanin halinki."
Gyada kaina na yi a hankali na ce.'' Kun kyauta kai dashi ai."
Ya yi bismillah yana cewa." Towon nan tun kafin na yi loma  guda yawuna ya tsinke wallahi."
Yadda ya tallafe filat din a hannunsa shine abinda ya ba ni dariya na tashi ina fad'in." Ka dai ci a nutse kada ka 'kware."
Bai ce mini komai ba ya cigaba da cin abinsa na zauna gefan katifa a nutse na janyo akwatin kayana na shiga duba kayan da zan sanya na yi wankan tun d'azu amma ban samu sukunin canza kayan ba ballantana na yi sallah. Na ji dai dadin ganin yadda jikin nasa ya yi sau'ki gashi nan har ya zage yana cin abinci.

Cikin rashin sukuni na gama shiryawa domin a jikina na ji cewa kallona yake yi. Ina juyowa kuwa muka yi ido hud'u da filat din towon a hannunsa yana ci yana kuma kallona kamar wanda ya samu tibi. Na d'an zumbura baki can k'asa-kasa na ce." Ni kam wane irin kallo ne wannan?"
"Me ki ka ce?"
Shiru na yi ban ce komai.  Sai ya cigaba da cewa." Kin ce idan ni maye ne na ci kaina ko?"
Da sauri na dube shi da mamaki a tare da ni." Haka na fad'a?" Na ce cikin sigar tuhumarsa. Sai kuwa ya daga kansa." Eh mana haka ki ka ce ai na ji, yanzu kuwa zan zo na cinye ki, ai kin ba ni magani na yi ras da ni, sannan kin ba ni towo da tantakwashi me ki ke tsammanin zai faru?"
Dariya maganarsa ta ba ni, na ce." Kana nufin ka warware kenan, muryarka fa har yanzu bata fita sosai."

Yana sud'e yatsun hannunsa ya ce." Za ki tabbatar da haka idan ki ka ji ni a jikinki."
Na ce." Ai ba ka fara ba, domin kuwa gidan nan bashi da wani tsaro kai ka san kanka ni ma nasan wanene kai ."
Ya yi shiru bai tanka mini yana cigaba da sud'e hannunsa na ce." Wai miyar ce ta yi dadi ko towon?"
"Duka sun yi dadi wallahi kin biya ni sosai yanzu abinda ya rage kawai ki cikashe ladanki ki ba ni kanki?"
Girgiza kaina na yi kawai Ina dubansa. Wani irin mutum ne da bashi da ta ido sakaka yake sakin maganarsa babu kunya balle kawaici.

Muka fara bugawa dashi domin akan sai ya kwanta da ni fa acewarsa towon da na bashi ne ya tayar masa sha'awa ni kuwa nasan ba haka ba ne kawai neman fitina yake yi tunda ya samu kansa mura da zazzafin sun yi sau'ki, na riga na san da wahala dama hakan bata faru ba sanin hali yafi sanin kama.
Ya rufe d'aki gam! ni kuma ina jin tsoron yarinyar nan ta ji shiru ga d'aki a kulle ta gane wani abu muke yi. Ni kaina a cikin buk'atar nake nasan kuma yadda na tara sha'awa haduwarmu ba za ta yi kyau ba.
Ganin yadda nake ta fargaba akan kada yarinyar ta fahimci wani abu da farko yana magana a hankali sai ya fara daga muryarsa tunda ya lura ba na son hakan yana cakumo ni da kokawa, takaici da b'acin rai suka dame ni, na rasa yadda zan yi dashi duk ya yamutsa ni gabad'aya rigar jikina ma ya cire mini.
Hawayen takaici suka dan zubo mini a kumatu a mai hali baya fasawa. Muna tsaka da hakan aka kira wayarsa hakan ya ba ni damar kwacewa a gaggauce na d'auki rigata ina sanyawa a jikina.
Hauwa ce ta kira wai bata da lafiya bayan haka kuma gidan ya yi mata girma.
Ban jin amsar da zai bata ba na fita daga d'akin da saurin gaske tsakargidan na samu Yusura tana kwance kan tabarma tana kallo a wayata.
Na sauke ajiyar zuciya cikin yakini da amincewa ba ta ji abinda ya faru ba tunda da alama kallon ya d'auke mata hankali. Na zauna gefanta muna kallon tare amma hankalina kaf yana kansa. Ina dan jin motsinsa da amsa kiran waya jefi jefi.
To a takaice dai a ranar da yamma aka sallami Gwaggo daga asibiti Hamusu ya zo ya sanar da ni cewa yanzu tana gida kuma babbar yayarsu da take aure a kamaru ta zo yanzu haka suna tare da gwaggon. Na ji dadin zuwa Yaya Talatu da yake haka muke kiranta a can kamaru ta yi aure da yaranta hud'u shiyasa ba sosai a ake ganinta ba sai da gagarimin dalili tun bayan rasuwar Yaya Amina bata sake zuwa ba sai yanzu. Na tabbatar kuwa ba zata koma ba sai jikin Gwaggon ya kara kwari da izinin Allah.
Hamusu kafin ya fita ya tambayeni Yallabai na ce masa Yana ciki Yana hutawa.
Koda na koma d'akin sai na same shi akan dadduma ya idar da sallar la'asar muka had'a ido na yi saurin shigewa bandaki na d'auro alwala na fito fuskata a d'aure bai sake birjiro mini da wata fitinar fa ganin yadda na keta bata

raina  sosai ya ce na bashi ragowar shayin da na yi masa alkawari. Na hada masa da zafinsa rau na ajiye a gabansa sai bi na da ido yake yi ina sake cin kunu......✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen  gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta

izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*47*
Ni kaina nasan abinda nake yi din bai kai a ce ya kyaleni dan shi ba sai don ya ga rashin dacewar hakan akaran kansa shiyasa ya janye fadi ma yake yi

ya gaji da zaman gidan so yake dare ya yi yayi tafiyarsa. Uffan dai ban ce masa ba domin ba na so kuma wata magana ta yi tsayi a junanmu.
A nan din ya yi sallar Isha'i, ya ce na d'umama masa ragowar towonsa na yi masa yadda ya buk'ata ya zauna ya ci sosai ya kira Sukairaju a waya suka yi magana duk ina zaune minti talatin ya iso har kofar gidan.
Nan na fahimci ya kira shi ne domin ya ja shi a mota. Da zai tafi bai sake tayar mini da wata magana ba, sai kuma jikina ya mutu na d'auka zai sake yi mini maganar zabar gidan da zan zauna kamar yadda ya bukata. Cikakkiyar sallama ba mu yi ba ya kama hanya zai fita, na bi shi a baya da agogonsa da ya manta a kan katifa. Ya kar'bi abinsa kawai ya yi gaba, hakan da ya yi sai ya tsaya mini a rai, ita gaskiya d'aci gare ta, ban ga abin jin haushi ba tunda iyakacin bakin kokarina na yi masa.
Koda na idar da sallar Isha'i sai na kira Sahura na ci sa'a ta daga muka gaisa na ce." Kin daina jin haushina kenan?'
Babu annashuwa ta ce." Ba zan daina jin haushinki ba sai kin gyara halinki."
Ina dariya na ce." Wani hali ne da ni mai muni Sahura."
Shiru ta yi mini ba ta ba ni amsa ba, na ce." Mutumin fa anan gidana ya kwana".
Da mamaki ta furta." Da gaske ?"
"Wallahi bai jima da tafiya ba ruwan jiya da daddare ya d'an same shi?"
Tana jimantawa ta ce." Amina kin samu kan bawan Allan nan wallahi ki ji tsoron Allah, ban ga namijin da yake bibikon mace kamar na ki ba, ki zauna ki yi nazari ke kanki kin san idan baya tsananin sonki ba zai ta'ba yarda ya kwana a wannan gidan na ki ba.
Ina dariya na ce." Haka ma Anti Yagana ta fad'a ni kuwa jinku nake yi ni nasan wanene shi, amma kin san wani abu ya ba ni tausayi ni kaina wallahi ba ki ga yadda ya sha wahala jiya ba saboda dukan da ruwa ya yi masa ya lafke zazzabi mura tari da ciwon kai da kyar muka rintsa ga uban sauro da zafi a d'akin."
"Humm! ki bari dai ya k'wace miki za ki yi kuka wallahi."
"Ba wani kuka da zan yi Sahura ha'kuri da juna muke yi ni dashi fa kuma kune kuke ganin kamar ni nake cutarsa, mu bar maganar nan haka sis tunda kin kasa fahimta amma ina so ki san da cewa amaryarsa na d'auke da juna biyu d'azu yake gaya mini."
"To shine me? kema Allah Ya ba ki naki rabon ba shikkenan."
"Sahura ba na jin fa zan yarda na sake haihuwa haka kawai ba zan yanki tikitin wahala da hannuna ba."
A takaice ta ce." Shikkenan ai." Yadda ta fad'i maganar shi ya tabbatar mini da cewa cikin takaici take ta ce." Wanki fa nake yi ki ka kira waya zan kashe."
Na ce." Da daddare wanki Sahura?'
"Ina da me yi mini ne?''
Ta ba ni amsa a kufule?"
Na ce." Ki had'a ki bayar zan biya."
"A a, ni menene amfanin lafiyata."
Na ce." Na ga alama rigima ki ke nema Sahura a ina zan samu mai kunshi ne?''

"Muna da su anan sosai."
Na ce." To ko za ki turo mini ita ta zo ta yi mini."
"Idan hakan ya yi miki  sai na turo ta."
Na ce." Duk abinki dai ba zan yarda na yi fad'a dake ba Sahura."
Ta ce." Dama kin ji na ce miki mu yi fad'a, ai gaskiya d'aci ne da ita."
Tafad'a tana d'an jan tsaki.
Na ce." Ai na ji shawararki shiyasa ma na amince zan cigaba da zama dashi gashi har ina neman mai kunshi haihuwa ce dai na ce ba zan yi ba."
"To kada Allah Ya sa ki yi, idan kin samu cikin ki zubar kawai."
Ta datse kiran ba tare da na farga ba.
Dariya na dinga yi mamakinta ya rufe ni wai lallai sai ta gaya mini bakar magana alhalin ba ita za ta yi mini zaman auran ba, mai d'aki shi ya san inda yake yi masa yoyo.

To ashe da ya fita daga nan mutumin nan wurin Babanmu ya je. Ban san abinda ya gaya masa ba, ni wajejen tara da rabi gama wayarmu da Sahura da kadan  Babanmu ya kira ni ya rufe ni da fad'a har muryarsa tana rawa yana fad'in idan na janyo masa zagi a gari sai ya yi mini Allah ya isa tunda hakki na uba ya sauke mini amma ina nema lallai sai na guji aure na yi zaman kaina, muddin wannan hanyar zan bi to zai zare hannunsa daga kaina.
Ban yarda na yi jayayya dashi ba na dinga bashi ha'kuri har sai da ya huci na kuma yi masa alkawarin bin umarinsa.
Na jima ina jajanta lamarin yadda babanmu ya hasala yana nema ya yi mini baki shine abinda ya fi daure mini kai, Ina ganin da ya tsaya mun gama magana a tsakanimu zai fi ba wai ya yi yun'kurin had'a ni mahaifina ba.
Ba ni da lokacin tambayarsa akan dalilin da ya sanya ya yi mini haka hujjarsa kawai bukatarsa ta biya ta kowace hanya bai yarda da abinda ya aikata zai bata mini rai ba.
Da takaicin hakan na kwana a raina don har na yanke shawarar kiransa a waya na tambayi jikinsa amma hakan da ya yi mini yasa na share shi ban neme shi ba.
Da safe ya kira waya na d'auka muka gaisa ya fara tambaya ina maganarmu ta kwana. Na nuna masa ban san maganar da yake nufi ba.
Ya ce." Maganar barin ki daga wannan gidan naki." Na ce." Yadda ka ce haka za a yi."
Ina ji ya sauke ajiyar zuciya tabbacin maganata ta faranta masa ya furta." Zan zo da daddare saboda gudun idanun jama'a, kamar yadda na fad'a sai mu je ki za'bi gidan da za ki tare."
A takaice na ce." Sai ka zo?"
Ya ce." Na gayawa Hajja tare muke dake kina can gidanku idan na zo sai mu je can ku gaisa ko?"
"To, kawai na ce masa.
Na kasa daurewa dai na furta." Na gaya maka duk irin abinda za mu yi ni da kai ka daina  had'a ni da mahaifina menene ribarka ta yin hakan, ai ni ba na gayawa mahaifiyarka abinda zai daga mata hankali."

"Ni ma na gaya masa ne domin na rasa yadda zan yi dake, nasan shi kadai ne zai tursasaki ki bi umarina tunda ni kin raina ni, Amina ai ba zalinci a zamantakewar auranmu, to ni ma don Allah kada ki zalince ni, sakin da na yi miki kuskure ne da zafin kishi ba zan boye miki ba ina mutukar sonki wallahi akwai kuma wani bakin kishi da yake damuna akanki idan ya motsa mini ni kaina tsanar kaina nake yi balle wanda zai kusance ni. Maganar nan ta mutu haka kada wanda ya ji, in sha Allahu hakan ba zata sake faruwa muddin kin kiyaye faruwar hakan anan gaba.
Maganganunsa suka kashe mini jiki, tabbas kowane dan adam yana da dabi'a, kuma yana kuskure babu wanda ya cika cif kuma ha'kuri a rayuwar duniya ya zama dole mussaman a zama na aure.
Dukda namiji ba a cika yarda dashi dari bisa dari ba, amma a wannan karon na dan ji tausayinsa kad'an kuma kalamansa sun yi tasiri a gangar jikina ya gaji zaman lafiya yake nema.

Sahura duk da ba mu rabu da annashuwa ba jiya sai da ta turo mini mai k'unshin da kwatance ta zo har gidan tunda bashi da wahala a bakin titi yake.
Yarinyar ta iya kunshi sosai ta yi mini kafafu da hannuwa ja da baki wanda rabona da lallai tun na haihuwar baby Khadija. Sosai na fito kamar wata amarya na bata dubu goma Yusura ta je ta rakata bakin titi.

Da ya zo bai shigo ba ya kira ni a waya ya ce na fito na same shi. Hijabi nasa har kasa na rufe fuskata da nikab da zan fita na ce Yusura ta kulle gidan ta ciki idan na dawo sai na buga.
Can tsallake na hangi motar wata kala ce daban domin bata nuna alamun tasa ba ce wata'kila ya yi hakan ne domin kada jama'a su gane wanene tunda duk motacin da yake tu'ammalli suna da alama wannan babu wata alama sai ta lamba. Sukairaju na jingine a jikin motar shi ma fuskarsa rufe da fece mark.
Ina karasawa ya risina mini muka gaisa  kafin da sauri ya bud'e mini motar na fara ko'karin shiga yana hakimce cikin k'ananun kaya da rigar sanyi mai kauri a sama. Kansa sunfuke da hula irin ta sanyi har kunne ya rufe idanuwansa sakaye da gilashinsa na ka'ida.
Na zauna sosai kafin Sukairajun ya shiga ya ja mota.
A hankali na furta." Barka da dare, ya jikin?"
Yana kallona ya amsa "Barkanmu dai ya gajiya?"
Shiru na yi ban bashi amsa ba, shi ma bai sake magana ba wata'kila ya yi hakan ne saboda kusantuwar Sukairaju tunda kallon da ya yi mini da farko shi ya tabbatar mini da cewa akwai magana a bakinsa.

Gudun aure littafin kudi ne. Yi kokari ki sauke nauyi muddin kina karantawa

Gidansa na unguwar sharada kwanar ganduje wajan gidan Hajiya Mariya shi ya fi kwanta mini a raina dalili akwai alkarya a wuraran kuma daf da titi ne,

bayan haka kuma ya yi kusa da wajan gidan Sahura dukda akwai 'yar tazara amma dai ba sosai ba za mu dinga samun sau'kin ganin ganin juna mussaman daga bangaranta.
Gidane iya gida wanda aka narka dukiya wurin gina shi, gini mai k'wari da nagarta da kuma ababen more rayuwa sabo ne ga dukkanin alamu ba a jima da gama aikinsa ba. A gyare yake ko'ina sai da ba a shirya shi da furnitures ba da sauran kyale-kyalen zamani gidan ya yi mini sosai domin bai kai girman na legos ba ya yi daidai da zama babu tsoro da fargaba.
Ya ce tunda shi na zaba to  shi ma ya yi masa gobe kuma zai sanya a shirya mini komai na ce to shikkenan. Muka shishiga ko'ina muka  duba muka hau saman benan ya bud'e wani d'aki a saman wanda shi kadai ne a dan shirye shi ma ba komai ba ne sai babban kafet da tuntu manya manya irin na sarauta uku, da manyan labuleye da suka kewaye d'akin.
Muka shiga d'akin yana gaya mini watani shida da suka gabata ya yi wani bako daga kasar senegal shine ya sauke shi a d'akin a dalilin tsaro da rashin yardar mutumin wai ya ji labarin najeriyar ta lalace da 'barayi masu satar mutane shine yake jin tsoron zuwa ya kwana a hotel. Anan ya sauka tsayin sati hud'u har ya kammala abinda ya kawo shi ya tafi.
Dariya kawai na yi domin nasan mutumin yana da gaskiya najeriya ta lalace sai da ta katsan-tsanan.
Ganin ya nemi wuri ya zauna har da kishingida a jikin tuntu na ce masa yana da kyau ya tashi mu tafi saboda dare ya fara yi goma har da minti biyar ga gari na damuna, ga kuma yarinyar mutane na bari a gida ita kadai.
Bud'ar bakinsa sai kawai ya ce." Ai kin zo kenan Hajiya kayanki kawai zan tura Sukairaju yanzu ya d'auko miki." Ya fad'a babu alamun wasa.
Da mamaki mai yawa a tare da ni na ce." Kai ma kasan hakan ba mai yiwuwa ba ne, ko ka manta da cewa na bar yarinyar mutane a gida, kuma me yasa Sukairaju zai je ya d'auko mini kaya ba ni da sirri ne, ai ba haka muka yi da kai ba.
Ya tashi zaune sosai yana kallona ya ce." Ba mu yi haka ba, amma yanzu na yanke hukuncin yin hakan domin ban ga amfanin komawarki wannan gidan ba tunda babu wanda za ki yi wa sallama."
Raina a b'ace na tsaya kawai ina dubansa gabad'aya ma bakina ya mutu da masifar takaicinsa na rasa ma wane nazari zan yi.
ya yun'kura ya tashi yana ce wa. " Tunda ba ki aminta da Sukairaju ya d'auko miki kayanki ba ni ne ba kya so ba huta to zan koma tare dashi zan had'o miki kayan tare da yarinyar shikkenan ko......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*

*V-VIP AREWA PEN✍*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*👇👇
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*

*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma,  dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce  dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*49*
Zuwa la'asar gidan ya shiryu ta ko'ina har kicin komai ya ji, da alama masu aikin sun jima suna murza zaransu domin ni na d'auka za su iya kaiwa dare basu gama ba.
Suka tattara kayan aikinsu suka tafi lokacin ma shi maigidan yana bacci saboda ya sha magani. Ni da Yusura muka zagaye ko'ina dakuna ukun da suke falon dukkunnsu a shirye kowane da set din gado kewaye da labuleye masu kyau falon set din kujeru biyu ya ci masu kyau da tsada da labuleye wad'anda suka dace wurin tibi ma yasha ado mai d'aukar hankali ko'ina hasken fitilu irin na zamani sun shirya mini kicin dina tsaf duk abin buk'ata babu wanda babu da alama kamfanin sun jima suna yi masa aiki.
Sukajiru ya dinga shigo da kayan abinci yana jibgewa a store din dake cikin kicin din da yake da yalwar gaske.
Gidan ya ba ni sha'awa sosai kuma daidai misali domin bai cika girma na d'aukar hankali ba sai dai an tsara shi sosai daidai zaman da babu tsoro kuma babu takura.

Da fargaba na tashe shi domin yin sallar la'asar ganin hud'u har da rabi ta yi nasan ba a yi masa gwaninta wani lokacin to amma ai babu biyewa son rai wurin take umarnin Ubangiji ina ganin idan har na bar shi ya cigaba da barcin lokacin sallar ya kure ina da lefi, bayan haka kuma shi kansa baccin gabanin la'asar ko bayanta Annabi ya yi hani dashi.
Ya tashi kuwa da d'an sau'ki jikin nasa don har gumi yake yi yana gabatar da sallar ya nemi abinci don da alama cikin magunguñan akwai wanda ya ke bud'a ciki kuma wai towon dawa irin wanda na yi masa a gidana.
Ban yi masa jayayya ba na fita na duba cikin store din duk kayan masarufin da Sukairaju ya zube babu na towo babu dawa balle alkama sai samovita sai shinkafar towo.
Na fita na sanar masa Ina dasu a gidana zan kira Hamusu yanzu sai ya je ya kawo mini. Da yake yana buk'ata bai ce a a ba.
Na kira Hamusu na yi masa bayani sosai yadda zai fahimta na kuma bashi kwatancen gidan, da yake dan halak ne awa daya da yan mintoci sai gashi a babur dinsa ya kawo mini komai.
Sosai ya ba ni tausayi saboda hidimar da yake yi a kaina ko ciki daya muka fito iyakacin abinda zai yi mini kenan.   Ya kuma ki tafiya wai lallai yana so ya gaisa da magidan kafin ya tafi. Sai na nufin saman zuciyata na dan bugawa na same shi yana waya da wani mutum na dan tsaya kimanin minti goma ya kammala kafin ya dube ni kadaran kadahan na ce." Hamusu ne yake so ku gaisa yana kasa na ce bari na nema masa izini."
Ya d'anyi jim kafin daga bisani ya ce." Ya shigo mana."
Na juya babu k'wari a jikinsa. Na same shi a falo suna dan hira da Yusura na ce .'Ka hau saman d'akin da yake kallonka yana ciki.."
Ya tashi da sauri yana fadin." Bari na sauko yarinya sai kin gaya mini sunan saurayinki tunda ni ba kya sona."
Na dube shi da mamaki yana hawa benan na dawo da kallona kanta sai sinne kanta take yi na ce." Cewa ya yi yana sonki ne?"
Ta daga kanta tana dariya kafin ta ce." E, mana, ni kuwa na ce masa ai ina da saurayina."
Murmushi na yi da cewa." A Ina saurayin naki yake ko shine dan gidan Yayar babanku wanda Sahura take gaya mini."
Ta daga kanta da kunya mai yawa a tare da ita. Na ce." Hamusu kenan shi ma ai da alkawarin auran wata a wuyansa  ko ta biyu zai yi dake ne?"
Da sauri ta ce.'' A a mama ni fa ba na son kishiya." Ta fad'a har muryarta tana rawa nasa dariya ina fadin." To shi wanda kike so din kina da tabbacin ba zai yi miki kishiya ba."
Shiru ta yi bata ce komai ba. Sai kawai na girgiza kaina na wuce kicin da tunanin halin kuruciya yarinyar.
Cikin nutsuwa na fara  gudanar da aikina gefe guda kuma ina cigaba da nazarin yanayin rayuwar nan ta duniya wato dai muddin kana raye  ka dinga ganin abubuwan al'ajabi da ban mamaki kala kala.
Muryar Hamusu na ji a kicin din yana fad'in." Anti ni zan tafi?''
Na juyo Ina dubansa yanayinsa ya nuna mini ba a nutse yake ba domin damuwa muraran ta bayyana a tattare dashi.

Cikin nutsuwa na ce." Shigo ciki mu yi magana."
Ya shigo yana sunkuyar da kansa kasa, tausayinsa ne ya kama ni har na ji kwalla ta cika idona tabbas mutumin nan akwai maganar da ya gaya masa wadda ta sosa masa rai da wahala ka ga Hamusu cikin irin wannan yanayin mutum ne mai ha'kuri da yawan fara'a ba ka taba gane yana cikin damuwa koda kuwa akwaita a tare dashi.
Na ajiye rariyar da take hannuna na ce." Ko ba ka gaya mini ba nasan abinda yake da akwai amma ina so ka sani ban goyi da bayan wannan zargin da ake yi maka ba, kuma duk inda za mu je ina nan akan bakana ban goyi da bayan a tozartaka ba a shirye nake da kare ka a ko'ina ba zan yarda a wulakantaka ba Hamusu na zauna dakai nasan halinka kiyashi ba zaka kashe da gangan ba balle har ka yi yun'kurin kashe mutum. Bincike dai ban hana shi ya yi ba, amma rashin  sanin wanda ya aikata ba zai sanya a gazgata cewa kaine ba, ai alheri ba ya zama sharri Hamsu ka samu nutsuwa kuma kada kada damu gaskiya zata bayyana.
"Wallahi anti gabad'aya a cikin fargaba nake ya za a yi na aikata wannan mummunan aikin me ya yi mini da zan yi yun'kurin kashe shi a yake gaya mini fa wai lallai da sanya hannuna wurin faruwar hakan, wallahi tallahi anti ban aikata ba, ai mutumin nan alheri ya kamata mu yi masa duba da abubuwan da yayi mana na sadaukarwa da taimaka ko k'aunar jininmu da yake yi ya cancanci sadaukarwa ta kowane fanni, shiyasa hidima idan tasa ce wallahi ba na gajiya koda kuwa zan kwana a tsaye. Na yi mamakin jin wannan furucin daga bakinsa anti duk da duniya ta lalace akan samu irin hakan amma wallahi ni ba na daya daga cikin butulayen mutane."
Na ce." Kada da ka damu Hamusu ka shige ka je ka cigaba da sabogiginka hankalinka kuma ya kwanta barazana yake yi maka domin akan bincike yake har yanzu shi ma bai gama tabbatarwa ba."
Ya girgiza kansa a sanyaye ya ce." Shikkenan anti ni ma kuwa ba zan bari ba wallahi zan tsananta bincike na kuma sanya ido domin tonuwar asirin wad'anda suka aikata hakan."
Na ce." Shikkenan hakan ya yi amma don Allah kada ka gayawa kowa maganar nan Hamusu ka barta cikin ranka." Ya ce." Na yi alkawarin yin hakan in sha Allahu rabbi anti.

To har na gama aikin zuciyata ba ta daina tsalle ba. Nasan idan na tunkare shi da maganar tutsiyar da ya yi wa Hamusu cibi ne zai zama 'kari dama mai neman kuka ne aka jefe shi da kashin awaki sai kawai na share shi ban nuna masa cewa nasan abinda ya yi ba.
Sai da na hada masa komai tukkuna na sauko daga saman na samu Yusura ta yi wanka ta shirya tsaf na ce taje ta d'ebi abinci wanka zan yi tukkuna.

Littafin gudun aure na kudi kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na shirya cikin doguwar riga ta atamfa duka kala shida na zo dasu hud'u sun yi datti saura biyu kacal itama Yusuran nata sun yi datti na ce da safe sai ta wanke mana tunda akwai na'uwarar wanki a gidan.
Sai komawa na yi saman a karon da ba zai lissafu ban ji matsalar hawa tunda kamar ina motsa jikina ne shiyasa hakan baya damuna.
Na sake samunsa yana waya amma cikin fushi da kuma kausasan maganganu da harshen nasara ya canza harshe sosai na yi tsam Ina kallonsa gabad'aya baya hayyacinsa gumi sai yanko masa yake yi na b'acin rai da kuma saukar zazzabin da yake dauke dashi
Fankar da ya umarceni da na kashe a d'azu da safe ita na kunna masa domin ita kanta rigar da take jikinsa daga baya ta jike da gumi.
Turanci yake yi tsantsa har yana hadawa da yaran chanis wanda ban ta'ba jinsa a bakinsa ba ashe komai dalili yake yi. Na d'an fahimci wasu abubuwan amma kasancewar ban ji farkon maganar sai na gaza fahimtar mai yake faruwa. Ba wai dukiyar ba irin wannan kalubalen da farautar rayuwar mutum shine abin damuwa.
Ya kai karshen maganar da bada umarni a rufe kamfanin gabad'aya na fi tsammanin wata matsalar ce kuma take shirin kutso masa bayan ga wata ba a kashe ba. Wannan kadai sun isa su hargitsa masa lissafi..
Ya kira Sukairaju a waya minti biyar ya shigo ya ce masa maza ya je Danbatta gidan Hajja ya debo masa kayansa na sanyawa da ya zo da su da laptop d'insa ya bashi key din d'akin.
Bayan fitarsa ya dube ni Yana fad'in." Ki sama mini ruwa na yi wanka na samu sau'ki."
Na ce." Ai wanka ba naka ba ne yanzu koda kuwa da ruwan d'umi ne saboda kada kuma zazzabin ya dawo."
Cike da tsawa ya furta." Sai na yi ta zama cikin zuffa ina tsami kenan malama ki yi abinda na ce ko na tashi na yi da kaina, ai Allah Ya hore mini hannu." Ta'be baki na yi na
tashi na sauka kasa ina mamakin abin daga shawara sai masifa da bakar magana.
Sai dana sauka kasan sannan na tuna akwai bandaki a cikin d'akin da yake na sake komawa sai na same shi a toilet din yana kwance shaya wadda ni a tunanina ma kwata kwata bata aiki sai naga ruwa ya kashe ya fara ko'karin cire rigar jikinsa. Shiga na yi bandakin na bude shayar ruwan da yake zuba bai cika sanyi ba da yawa zai yi daidai wanka a yanayin tunda ba zafi ake yi ka'in da na'in ba kuma ba sanyi ake yi ba.
Ban ce masa komai ba na fice daga bandakin domin zuciyata ta fara yin zafi akan abinda yake yi mini duk kuwa da ko'karin da nake yi akansa
Ban sake hawa saman ba domin ina ganin yin nesa dashi din zai fi mini kwanciyar hankali muddin bashi ya neme ni ba.
Yusura tana falo a kwance cikin kujera tana kallo a wayata ashe finafinan da Yusi ya uzzura a tura a wayar za su yi rana.
Na kar'bi wayar domin Ina son kiran anti Yagana dalilin damuwar da take damuna. Komai na tibin dake falon a hade yake sai na kunna mata tunda na

lura ma'abociyar son finafinan indiyace na kamo mata tashar da suke yin fassarar hausa. Ta kuwa gyara zamanta sai kace mai d'aukar darashi.
Cike da mamaki da zullumi anti Yagana ta furta." Hamusu ba zai aikata wannan d'anyan aikin ba Amina, a dai kara bincike da kyau a jikina nake jin hakan akwai dai makarkashiya amma ki bi komai sannu a hankali kuma don Allah ki dinga tausar zuciyarki akan mutumin nan ki yi duba da yanayinsa da al'amuransa na yau da gobe wasu abubuwan dole a yi masa uzuri ki bari ya samu nutsuwa ta bangaranki koda ya yi miki abinda ranki bai so ba ki tuna alherinsa ki yafe masa, ki yi kokarin ri'ke auranki domin a yanzu dai samun makamancinsa zai yi wahala Amina kuma mazan duk haka suke wallahi kwaryaar sama ce take dukan ta kasa kusan duk haka halinsu yake....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*

*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari  ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har  Madiga  tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma,  dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce  dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba  fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan  zannuwan Gado da carpet*

*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456
*48*
Shiru na yi ban iya cewa da shi komai ba. Ya d'auki gilashinsa da ya ajiye ya sanya ya tashi yana sa takalminsa hanyar fita ya nufa na bi shi da ido ina jin wani bala'in takaicinsa, da gaske dai yake na zo kenan amma mutumin nan mugun dan rainin wayo ne, shiyasa wasu lokotan baya ba ni tausayi.
Zamana na yi gabad'aya jikina babu k'wari na fito da wayata daga cikin jaka ina dubawa goma da minti ashirin a ganina yanzu kafin su dawo har sha daya na dare ta yi. Ni hankalina ma ya fi tashi akan yarinyar mutane da take amana a hannuna
Ina nan zaune tsit babu motsin komai sai uban hasken fitilu a ko'ina, tsoro ya dan shige ni na zame na kwanta a hankali ina kiran sunan Allah kad'aici ko kad'an bashi da dad'i
Wajejen goma da minti arba'in kira ya shigo wayata na duba sai na ga lambar Sukairaju ban kawo komai ba na d'aga na ji shi cikin tashin hankali .
A tsorace da kidima na tashi zaune." Hatsari Sukairaju Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! na tashi tsaye da wayar a kunnane yana fad'in." Ki d'an samu nutsuwa duk muna lafiya babu wanda ya samu mugun rauni Yallabai ne ma ya samu targad'e a 'kafa. Hawaye ya fara sauka a saman fuskata na ce.'' Ita yarinyar fa ina fatan lafiyarta lau, kuma ya aka yi hakan ta faru? kuna Ina yanzu."
Ya ce." Ga mu nan bakin titin rijiyar zaki wajan Musa iliyasu.
Na ce." Garin yaya haka ta faru Sukairaju ina Yallabai din bashi wayar ina so mu yi magana."
Shiru na ji sai tashin iska gabana yana ta bugawa na ji gyaran muryarsa kafin ya ce." Babu wani ciwo mai muni fa ki kwantar da hankalinki."
Na ce." Yanzu kuna Ina ku dawo gida don Allah dare ya yi ina Yusura tana nan lafiya ko."
A nutse ya ce." Gata nan kusa da ni tana lafiya babu abinda ya sameta, ni ne ma na yi gocewar
'kashi a k'afata za mu zo yanzu."
Ya kashe wayar bai jira jin abinda zan sake fadi ba.

Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

A tsaye na wanzu har Allah Ya sa suka shigo gabad'aya Sukairaju da akwatin kayanmu ni da Yusura shi kuma yana dan jan kafarsa amma jikinsa kalau daidai da gilashinsa yana idonsa.
Zuciyata ta dan yi sanyi na dubi Yusura sai zare Ido take yi kamar ma a tsorace take idonta da alamun kuka.
Na kama hannunta muka shiga d'akin ta zauna jikinta a sanyaye. Shi kuma yana can nesa saman kafet tunda d'akin da girma sosai yana tattare kafar wadonsa da ya ji ciwo. Na tsaya kawai Ina dubansa ina jin wani iri a a jikina,

na san akaina duk wannan abin ya same shi, ina ganin idan ban yi hakuri na zauna dashi cikin ko wane irin yanayi ba Allah zai iya saka masa.
Sukairaju ne ya shigo ya ajiye kayan a gefe, shine kuma ya gyara masa targadan tunda ba yadda bai yi dashi ba tunda lamarin ya faru su wuce asibiti a duba shi wurin da ya goce asa magani ya ce a a baya son haniyar jama'a, za su dame shi da zuwa dubiya harda masu neman labari tunda abin ya faru cikin dare wajan da babu idananun jama'a sosai kuma ba a fahimci wanene ba kawai magana ta mutu motar ma a can suka barta bakin wajan da abun ya faru suka shigo babur din adaidaita sahu. Mamaki mai yawa ya kama ni. Lallai na yarda soyayya babu abinda bata sanyawa, tana k'askantar da mai mulki mai saurata attajiri mai ilimi da sauransu.
A wannan ga'bar na jinjina masa sosai kuma na yaba masa har cikin raina.
To shi dai Sukairaju ya san mota lafiyarta lau tunda sabuwa ce bata da wata matsalar komai amma bai san ya akayi har 'kososhin tayar baya suka kwance ba sai da lamarin ya faru wanda Allah ne kadai ya auna arziki da sai da a ji mummunan labari tunda  sitiyarin motar da ya k'wace daga hannunsa kifawa motar ta yi da kyar suka fito.
Kwana muka yi ba mu rintsa ba muna tattauna maganar ni da shi yana zargin dai akwai masu bibiyarsa tun bayan zuwansa zai dai tsananta bincike.
Da gari ya waye muka tashi da gyara masu aiki suka zo domin su kintsa gidan.
Sukairaju ya fita ya samo mana abinda za mu ci. Da muka yi waya da Hamusu na gaya masa yadda akayi amma ban fad'a masa tsautsayin da maigidan ya samu ba ya ce zai zo da yamma.
Yusura kam yarinyar na da nutsuwa kasa zama ta yi tare damu a d'aki daya bacci ma jiya dan barawo ne ya sace ta kuma don ba yadda za ta yi ne ta kwana a d'akin wai sai ta fita sai da na yi mata jan ido tukkuna na nuna mata gidan sabo ne ko ta fita babu d'akin da za ta samu a kintse balle ta kwanta shine ta takure a wata kusurwa ta rufa da hijabinta. Da safe kuwa ta fice wai zata duba gidan .
Jiya dai da abin ya faru jikinsa lafiya lau banda targadan da ya yi sai kujewa a daf da gwiwarsa bayan wannan kam babu wata matsala sai da garin ya waye kuma ya fara kuka da ciwon ga'bo'bi na ce masa asibiti ya kamata ya je a duba shi sosai ko da daddare ne tunda yana gudun idonanun mutane wata'kila akwai abinda ya bugu a jikinsa ya ce ba zai je ba na kyale shi kawai. Gabad'aya na rasa yadda zan yi da sha'aninsa jikinsa ya nuna alama yana buk'atar ganin likita.  Ya d'auki wayarsa Ina zaune ya kira Sukairaju wallahi na zaci ya d'auki shawarata ne ashe ba haka ba ne, koda Sukairaju ya shigo sai ya rufe shi da fad'a irin wanda  ban ta'ba ganin ya yi masa irinsa ba domin kuwa a cikin yaransa na tabbatar da cewa yana sonsa kuma tasu ta zo daya. Fadi yake yi da kai za a had'a ba ki a kashe ni ko Sukairaju me ya sa na d'auki amana ragamar kula da rayuwata shige da fice na da duk wani motsina amma za ka bada goyan bayan cutar da ni, ban aminta da kai ba a wannan ga'bar jiya na yi maka shiru ne domin ban gama nazari akan faruwar wannan lamarin ba, yanzu zuciyata ta amince mini da hadin bakinka wajan ganin kun kai ni kasa  in banda kai babu wanda ya san na shigo garin nan ya

aka yi har k'ososhin jikin sabuwar motata za su zube baka sani ba, ina kake ina ka ajiye motar ? Kai ne ka cire k'ososhin ko kuwa wani ka biya ya cire domin biyan buk'atarku wannan amsar nake so ka ba ni tun muna biyu ni dakai ka fito ka gaya mini asalin abinda ya faru.
Ya zube a gabansa cikin tsananin damuwa da tashin hankali yana cewa." Wallahi Yallabai ban san yadda aka yi ba, kuma zargin da kake yi mini ba haka ba ne, ba ni da niyyar cutar dakai Yallabai shekara nawa muna tare menene ban samu ba ta dalilinka, babu abinda ba ka yi mini ba na rayuwa idan ma na cutar da kai nasan Allah ba zai barni ba, a ko'ina ne zan iya sadaukar da rayuwata akan taka rayuwar ni dai nasan lokacin da muka koma unguwar domin d'aukar kaya daka bar ni a bakin mota ka shiga gidan na dan zaga baya domin yin fitsari da na yi sai na fito sai na tsaya sayan lemon fata anan bakin titin dai shikkenan abinda na sani, ina kuma tunanin wannan damar aka samu har ka cire k'ososhin motar ni kaina ranka ya dad'e na fara zargin akwai hannun Alhaji Sammani a ciki dalili nasan tunda ka rubuta masa takardar sallama ba zai ta'ba ha'kura ba mutum ne ma'ketaci wata'kila yana bibiye da kai har ya gano kaine ake d'auka a motar dukda boyewar da ka yi, kuma ranka ya dad'e jama'a da yawa sun san kana garin nan tunda shekaran jiya mun shiga asibitin Malam Aminu cikin motocinka wanda kowa ya sanka dasu, to ka ga bibiyarka ba zai yi wa wanda yake burin cutar dakai wahala ba.

Jin ya yi shiru kansa a kasa shi ya tabbatar mini da cewa maganganun Sukairaju sun kar'bu a wurinsa. Na ce." Kada ka yanke hukunci cikin fushi, ka yi bincike dukda abin akwai rikitarwa amma ba na tsammanin za a had'a ba ki da Sukairaju a cuce ka."
Ya dube ni kafin ya ce." Za a had'a ba ki da Hamusu kenan?"
Da tsananin faduwar gaba na ce." Hamusu kuma?"
"Kwarai kuwa bayan shi wanene makusancinki?wanene ya kawo ni gidanki ta yaya za a kwance wasu daga cikin k'ososhin dake jikin tayar motata babu sanin Hamusu."
Na gyad'a kai da zullumi mai yawa a tare da ni na furta." Ba na tsammanin haka ranka ya dad'e, dukda dai ba a shedar mutan amma Hamusu ba zai aikata hakan ba."

"Me yasa kai tsaye ki ka fad'i haka umm?" Ya fad'a idonsa a tsaye akaina cike da zallar tuhuma da mugun zarginsa da ya motsa.
Shiru na yi domin kuwa ba na so mu jayayya agaban Sukairaju.
Ganin haka ya dube shi  tare da ba shi umarnin fita.
Ya tashi yana fad'in." Na gode Yallabai, amma ya kafar taka Ina fatan bata yi maka ciwo ko?"
A takaice ya ce." Ta warke Sukairaju na gode, kada ka yi nisa zan iya nemanka a kowane lokaci."
Ya d'an risina yana godiya kafin ya kama hanyar fita.
D'akin ya yi shiru ni fargaba da damuwa sun ishe ni, zuciyata nata tsalle da k'in rashin amincewa Hamusu zai aikata mini haka. Wata zuciyar tana ce

mini Amina makashinka fa yana gindinka, ba ki san menene a zuciyarsa ba zahirinsa kawai ki ka sani.
Hawaye masu zafi suka fara kasa tsere a kumatuna idan kuwa hakan ya tabbata lallai Hamusu ya cutar da ni ya zalinci kansa ya zalince ni, ya 'bata mini nasabar yarana."
Ya nisa kafin ya ce." Har yanzu ba ki yarda da maganata ba ko?"
Girgiza kaina na yi a raunane na ce." Ba wai ban yarda ba ne, abun ne kawai yake ba ni mamaki da al'ajabi."
Sai ya girgiza kansa yana fad'in." Ni ma zargi na ce Ina yi ba wai na ce shi din ba ne, amma dai kin san shine mafi kusa dake da ni, kuma shine ya yi mini jagora gidanki, kafin Sukairaju ya san inda nake wanene zai je ya kwance 'kososhin mota?"
Ina kuka na ce." Yanzu ka gama fad'a zargi kawai kake yi baka tabbatar ba, to me zai sanya ka tsaye ba tare da ka tsananta bincike ba ka nuna shine, kenan zargin da kace ka na yi bashi da amfani kawai ka fito fili ka ce Hamusu ne yake yun'kurin raba ka da duniya shikkenan sai  zambu da gugar zana su 'kare."

Ganin yadda  hankalina ya tashi da maganar da ya yi akan Hamusu ya sanya bai sake tashin maganar ba, amma nasan ba wai ya ha'kura ba ne ya yi shiru ne saboda bashi da tabbas akan abinda yake zargi. Ni kaina ba wai na ce Hamusu ba zai iya aikata hakan ba ne, ai da adam ne wanda yake tattare da ajizanci amma amincewa kai tsaye bashi ne adalci ba. Muna nan dai zaune ni dashi cikin rashin sukuni ya kira personal doctor dinshi  a waya ya yi masa bayanin yadda yake ji a jikinsa gabad'aya ko'ina ciwo yake yi masa ga rashin test a bakinsa da zazzabi kad'an. Doctor din ya ce zai yi masa text na magunguñan da zai sa a sayo masa domin yanayin bayanin da ya yi masa yana tunanin zazzabin maleria ne ke so ya kama shi.
Ban yi mamaki ba da farko kukan ciwon jikin da yake yi na d'auka tsautsayin da suka samu ne ya ce shi babu wani waje da ya bugu a jikinsa bayan 'kasan giwarsa da targad'an da ya yi. Tabbas zazza'bin kuwa zai iya kama shi sakamakon sauron da ya cije shi a gidana. Ya kira Sukairaju domin ya zuwa wajan sayar da magani ya sayo masa. Kafin shigowarsa na ce." Ni da za ka d'auki shawarata da ka je asibiti ba fa a wasa da lafiya."
"Ba ina da za  ni fa ." Amsar da ya ba ni kenan babu walwala a fuskarsa. Sai na yi shiru kawai na zuba masa ido yana da wani irin hali muddin bai so yin abu ba to babu wanda ya isa ya tursashi, ni kuma a tunani na zuwa asibitin kamar zai fi muhimmanci ko da yake wannan din ma ga dukkanin alamu babban likita ne tunda ba zai d'auki likitan da bai san aikinsa ba domin duba lafiyarsa ba....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta

Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*51*
Na dawo na same shi yana cigaba da aikinsa ammafa fuskarsa ta dan canza kad'an.
Hankalinsa na kan abinda yake yi ya ce." Kina jin mu da Hajja ko?'
Na nuna ban fahimci komai ba.
Ya furta." Wai itama Hauwa ta dawo nan tunda tana da juna biyu, Hajja tunda ta samu labarin cikin nan ta hana kanta sukuni, na ce mata a a dai ai ba zama zan yi ba wata'kila ma jibi zan koma."
Na ce." Me yasa kace mata a a, ta dawo nan din don Allah idan tare take so mu zauna ai da d'akuna idan kuma gidanta daban take so ai kana da iko, itama Hajja tana da dalili ai lokacin da nake rainon baby ta zauna mini."
Ya ce." Idan har Hauwa za ta dawo nan to ke za ki koma domin ba zai yiwu a ce ku nan ni ina can ba, idan bukata ta motsa mini matan banza kuke so na bi."
Shiru na yi kawai ban ce komai ba, ba na tsammanin zan sake komawa legos koda kuwa Hajjan ce ta bada umarnin haka.
Na ce.'' Yanayin yadda Hajja take magana ya nuna kamar a cikin bacin rai take shiyasa tun farko naso na je na gaisheta ta san da zuwana domin sai ta ga kamar ana 'boye mata wani abu ne. Na tare a sabon gida baka gaya mata ba sai 'boye-boye kake yi baka so a san kana garin nan ban gane dalilin yin hakan ba har yanzu."
"Dalilina na yin haka suna da yawa Amina, amma yanzu tunda mun sasanta ba kya jin haushina zan gaya miki na farko duk wanda ya ga jerin motocina na gidanki zai zargi wani abu rabuwar auranmu da nake ta b'oyewa duniya zata sheda hakan har ita hajjan ta ji labari gani can ina zawarcinki ke kuma kin koma zaman kanki irin na baya wanda mutane suka shede ki da haka. Za a yi ta yawo damu a duniya kowa na  tofa albarkacinsa bakinsa. Na gayawa Hajja cewa kin je can maiduguri biki ni kuma na ce mata zan zo nan domin duba Gwaggo wadda ta haifi mahaifin Yusi, ko da na sauka garin nan hakan na sake gaya mata.
Amma wannan ba abin da za a tsaya ana ta magana ba ne, zan yi magana da Inna Uwani a samu wata dattijiwar sai a tura mana ita can su zauna tare har Allah ya sauketa lafiya."
Na ce." Idan dai hakan zai janyo matsala don Allah Hauwa ta dawo nan itama ba na son abinda zai sa Hajja ta ga rashin kyautawata"
Babu damuwa ya ce." Idan kin aminta hauwa ta dawo ai abu ne mai sau'ki sai ta dawo din ke kuma sai mu koma tare "
Girgiza kai na yi na ce "A a ni kam ai na dawo kenan in sha Allahu."

Ya ce." To sai ki ja bakinki ki yi shiru tunda ke kin yi nasara amma ba zai yiwu a ce duk ku tattara anan waje daya ba.
Ya fita sallar azhar bai dawo ba ya bar wayoyinsa a d'akina ana ta kira na shiga d'akin a daidai lokacin da wani kiran ya sake shigowa na d'auki wayar na duba sunan Hadiza ne yake yawo cike da mamaki nake bin sunan da kallo. To kai tsaye dai ba zan yanke hukunci cewa Hadizar gidanmu ba ce tunda mutam ne na mutane akwai ma'aikata mata da suke yi masa aiki mabambamta har da k'warori. Ba yadda za a yi na daga wayar tunda akwai tsaro (security) sai na ajiye har ta katse wani kiran ya sake shigowa a k'alla akan idona sai da aka kira sau kusan shida kafin a hakura. Ya shigo a gurguje yana fad'in.'' Ban san me mutane suka zama ba a wannan duniyar ba ni da lokacin da zan 'bata akan yin jawabi dangane da Sammani abinda suka samu na shaci fad'i ya ishesu babu wata gidan jaridar da zan tsaya bata lokacina a kansa.
Na ce." Wani abun ne ya faru kuma?"
Ya zauna gaban abincin dana shirya masa yana cewa." Sun ankara da ni ne duk da na rufe fuskata da takunkumi yanzu bakin gate din gidan nan mutane ne cike manema labarai da mabukata."
Gabana na dan bugawa na ce." Akan me suke neman labari kuma?
"Dangane da abinda ya faru mana tsakanina da Alhaji Sammani suke neman jin ta bakina."
Na ce." Ka ja bakinka kawai ka yi shiru don Allah kada ka ce komai bayanin da ka yi da farko ya wadatar wata'kila wasu sun samu labarin ko ya yi yun'kurin kashe ka ta hanyar sanyawa a kwance maka k'ososhin mota."
Ya ce." Ba na tsammanin haka, lamarin dai da suka samu shine na salwantar mini da gidan gonata dake tiga da kuma sabon kamfanin da na fara ginawa a mariri wanda shi kadai ya san da ajandar hakan to akan hakan dai suke so su ji abinda zan ce."
Na ce." Ai ka ce ka yafe masa ba shikkenan ba. Mutane ne ba su san zaman lafiya shi kansa nasan yanzu yana can cikin jin kunya da damuwa ga kuma fargabar irin kallon da mutane za su dinga yi masa.
Ya ce." Ai idan har suna ganina ba za su daina bibiyata ba Amina, ba ki san dan jarida da na ci ba ko."
Shiru na yi ina kallonsa ya janyo wayarsa dake saman gado yana fad'in." Zuba mini abinci ina so na fita zuwa gidan hajja ina fargaba wallahi."
Na fara had'a masa abincin a tsanake na ce.' An kira ka a waya ka ga ni ko?"
Ya na duba wayar ya ce." Hadiza ce yayarki."
Na dube shi cikin nutsuwa." Hadiza kuma?"
Ya d'aga kansa a hankali ya sanya wayar a kunnansa kiranta ya yi.
Kaina ya kulle da mamakin lamarin dama tana kiransa ashe shiru na yi kawai domin na ji wannan karon kuma dame take tafe.
Gaisuwa suka yi ita dashi cikin girmawa har tana tambayata da Yusi shi ma ya bata amsa da kulawa tunda na fahimci duk abinda ya shafe ni yana bashi girma.
Magana take yi masa cikin rauni har da rawar murya amma sakamakon yadda muryarta ta yi kasa ban ji komai ba.

Na ji yana fad'in." Allah Ya rufa asiri in sha Allahu za a duba yiwuwar yin hakan, Allah Ya shirye shi da sauran masu hali irin nasa.
Ya kashe wayar yana dubana kafin ya ce." Kuna da wani d'an uwa wanda Allah Ya jarabta da rashin ji ?" Da mamaki mai yawa a tare da ni na ce." Ba mu dashi gaskiya anti Yagana ce babba a gidanmu a maza kuma Usani ne Hassan dinsa ya rasu.
Ya gyad'a kansa tare da cewa." Tana gaya mini dan'uwanku hukuma ta kama da zargin damfarar wani mutum miliyan hud'u da rabi."
Na ce." Shine me kuma? Ba zai wuce d'an'uwanta da na sani ba mamarta sai da ta yi aure a wani wurin har ta haihu sannan Babanmu ya aureta shine kawai abinda na sani.
"Tunda har Mamanta tana auran mahaifinku ai idan da kara shi ma d'an uwanku ne ko ba haka ba ne."
Na ce" Don girman Allah ka daina biyewa Hadiza bata da gaskiya fa, ba zan boye maka ba ko kwanaki nan karyar rashin lafiya suka shirya da Ummansu ita Fatin ma bata sani ba ka d'auki kudi ka basu har miliyan shida sannan kuma na ji labarin an ce ka bata jari har tana zuwa Dubai sarin kaya. kai baka gaya mini ba itama bata gaya mini ba, ko da yake ai ta san bata da gaskiya ba zata gaya mini ba, wannan ma ban yarda ba karya take yi wallahi."
Jim ya yi yana nazari kafin ya ce." Ta bukaci na taimaka mata kasancewar bata da aure dana tambayi matakin karatunta ta ce mini ko sakandire bata gama ba a gidanku ke kadai ce ki ka danyi karatu to kin ji dalilin da ya sanya na d'auki kudi na bata da niyyar ta yi jari domin ta tsaya da kafafunta a matsayinta na bazawara rashin sanar dake ba shi da ala'ka da wani abu tunda ni ban iya alheri na fito ina shela ba."
Da takaicinsa na ce." Don ka gaya mini sai ya zama wani abu to ta dalilin wa kasan Hadizan Ina ce 'yar'uwata ce."
Ya dube ni a tsanake kafin ya ce." Ni ba 'yar uwata ba ce kenan?"
Shiru na yi ina kallonsa. Ya girgiza kai bai sake cewa komai ba ya fara cin abincin dana hada masa.
Bakincikin abinda Hadiza take yi mini ya hana ni sukuni sai da na bari ya fita zuwa gidan Hajja tukkuna na kira anti Yagana muka gaisa na gaya mata maganar tariyata a sabon gida sannan na sanar da ita irin rashin mutumcin da Hadiza take yi.
Ta ce ai d'aurin gindin babarsu ta samu auran suke su gurgud'e miki Amina amma idan ba haka ba wannan ai zubarwa da kai mutunci ne tun mutumin nan yana yi musu kara da kawaici har sai sun kure ha'kurinsa ta zubar mana da mutunci wallahi "
Na ce." Anti Yagana Ina ganin kawai zan je gidan ne mu yi duk wacce za mu yi da ita gaskiya na gaji da abinda take yi mini wallahi ba zan jura ba.
Ta ce." Kada ki je yin hakan zai iya b'ata masa rai ai mai hankali ne shi ya san komai kawai yana biye mata na tabbata idan ya gaji ko saurarata ba zai kara yi ba.
Ki zuba mata Ido kawai saboda idan ki ka yi magana za a d'auka kece ki ke hana mijinki alheri shima kuma tunda bai gaji ba ai kudinsa ne ba na ki ba."

Gudun aure littafin kudi ne, kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Mafarin samun matsalata da Hajja kin amincewa da komawa legos kamar yadda ya zo yana gaya mini sun yanke shawara ita dashi akan ni na koma can din domin kula da Hauwa a matsayina na wadda ta yi haihuwa uku. A cewar Hajja duk da Hauwan nurse ce ai b'ata ta'ba haihuwa ba balle ta ce ga yadda take kuma koda ta zo haihuwar yana da kyau a ce da akwai wani a kusa da ita. Lokacin da ya zo yana gaya mini kawai jinsa nake yi da kunne domin na tabbatar da cewa zamana ne ba a buk'ata anan din saboda ya kafe kai da fata ba zamu tattaro mu dawo nan gabad'aya ba dole wata ta koma can tare dashi.
Na farko dai Hauwa ba yarinya ba ce a lissafin ma shekaru ma ta d'ara ni da kusan shekaru hud'u sannan kuma wace irin haihuwa ce ba ta gani ba, idan ba a shigo da son zuciya ba ina ganin ita kanta ma za ta iya kar'bar haihuwarta idan ta kakare ai akwai asibiti sai su je can, zamana babu wani abinda zai amfana tunda ba wani shiri muke yi ba to kamar dai yadda ya nemi alfarma wurin inna Uwani Ina ganin shine maslaha kawai a kai mata dattijuwa daga cikin danginsu.
Da har Hajja ta amince da da shawarar da ya yanke kafin ya bar gidan ta kira inna Uwani suka yi magana ita ta rusa shirin ta ce ita dai hankalinta sai ya fi kwanciya Hauwa ta dawo kusa har da yin kuka tana gayawa Hajja ai ta je ta taya ni rainon ciki har sai da na haihu tukkuna..

Assalamualaikum. Ina kwanaku ya gida ya yara. Ina fatan duk Kuna lafiya. Mun kammala book 3 Kuma typing din da na yi ya kare don haka za ku d'an yi mini ha'kuri na d'an wani lokaci sati daya ko 'kasa da Hakan in sha Allahu rabbi idan na tara wani da yawa sai mu cigaba. Na gode sosai da sosai Ina kuma fatan labarin Yana yi muku dadi fiye da yadda nake tsammani Amina ta ce tana miko gaisuwarta....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*52*
Wannan dalilin ya sanya Hajja ta ce ya gaya mini na shirya idan zai koma sai mu tafi a tare. Kuka sosai na dinga yi ina fad'in ba a yi mini adalci ba domin sai da na shekara daya a can kafin Hauwa ta tare me zai sanya kuma yanzu

a ce mini na koma saboda wani dalilin da bai shafe ni ba, iyakacin gaskiyata na gaya masa ba wai ina b'akinciki da haihuwar da za su yi ba, ina ganin kamar akwai son zuciya a wannan hukuncin dukda Hajja ta wuce ta nemi wata alfarma a wurina na turje mata to amma na riga na gama tabbatarwa da kaina cewa wannan hukuncin itama ta yanke shine domin son rai da kuma farantawa 'yar'uwarta ai ya gaya mini tunda aka samu cikin ta rasa sukuni idan zai yiwu ita din sai ta sake komawa ta zauna mata kamar yadda ta zauna mini ai ba hujja ba ce a ce dole sai ni zan je na zauna tare da ita tunda suna da yadda za su yi.
Rarrashin duniya babu irin wanda bai yi mini ba na ce ba fa zan bi shi ba domin da muna abun arziki da ita ne ma da sauki to kowa ta ciki na ciki me zai sanya na je na bautata mata daga baya wani sharrin ya b'ullo.
Ya nuna ai saboda shi zan yi, idan ma bai isa ba to na bi umarnin Hajja kamar yadda ta buk'ata kada na bijire, na ce ai ba ra'ayinta ba ne itama ta yanke hakan ne domin ta farantawa 'yar'uwarta rai.
Kwana da yini muna ta abu daya domin duk ta inda ya biyo nasan hanyar da zan zame kaina na nuna masa ba da hurumina ne ba, ni ma lokacin da na haihu 'yar uwata Hadiza ce ta zauna mini. Na kuma gaya masa ko da wasa kada ya sanar da mahaifina domin yin hakan zai janyo mana matsala mai girma saboda na riga na san halinsa sarai.
Itama anti Yagana ban gaya mata ba duk da mun yi waya da ita a ranar muna tattauna matsalar da ta shafe mu amma har muka yi sallama ban fad'a mata maganar ba.
Da yamma sai ga Hajiya Saratu na karbeta hannu biyu sosai muka gaisa dama can muna girmama junanmu akwai kuma kunya da kawaici sannan Ina ganin darajarta sakamakon tana da sunan Mamana.
shiyasa ko da ta fara yi mini maganar ban iya jayayya da ita ba kawai na yi shiru saboda ina jin nauyin na ce mata ba zan koma ba yanayin dana shiga ya nuna mata cewa ban yi na'am da abinda suke so ba. Jiki ba kuzari muka yi sallama ta tafi..
Sai da ya shigo gidan yake tambayata Hajiya Saratu ta zo na ce masa eh daga haka ban sake wata magana ba. Ya dinga bibiyata yana so ya ji abinda muka tattauna da ita bance masa komai sai da daddare tukkuna ya kira ta a waya a gabana suka yi Ina jin sautin maganarta tana cewa dashi idan zai yiwu kawai ya ha'kura tunda abu ne na lokaci Hauwan ta dawo tunda haka suke so saboda itama tana ganin kamar idan aka ce dole sai na koma an shiga shakkina idan ta haihun anan an yi taron suna sai ya tsara yadda zaman zai kasance idan ma za mu dinga zuwa can muna yi masa wata shida shida mu dawo hakan zai yi alheri.
Na fahimci azancin Hajiya Saratu kuma kamar ta zo da sasanci anan a wannan ga'bar zai iya ha'kuri tunda ta b'angaransu sun dage ya ha'kura ta dawo nan din har ta haihuwa abu ne na lokaci kad'an bayan ta haihu sai mu raba na je na yi wata shida idan na dawo sai itama ta je ta yi nata wattanin.
Ya kar'bi shawarar ne saboda gajiya da ja'ina daka kowane bangare amma na fahimci dan ba yadda zai yi ne ya amince ya fara shirin komawa amma cike yake da jin haushina acewarsa ni ce ya kamata na dubi halin da zai shiga

amma kishi da son rai ya hana ni yin abinda ya dace. Shiru kawai na yi masa ban tanka ba har ya kammala shirinsa babu cikakkiyar jituwa a tsakaninmu na yi ta so mu rabu cikin girma da mutunci yana bijirewa haka na zuba masa ido har ya kammala shirinsa ya tafi babu wadataciyyar sallama a tsakaninmu.
Bayan tafiyarsa da kwanaki uku Hauwa ta dawo a gidan Hajja ta sauka na samu labari ne a wurin Hajiya Saratu a lokacin dana kira ta a waya da kuma sutturuna na can da aka kawo mini na kira Hajiya Saratu ne a waya domin na sake wanke kaina tunda ita ta fahimce ni.
A ranar kuma na kira shi  duk da bai ne me ni ba, amma nasan yanzu ya huce daga fushin da yake yi tunanina ne ma ya rabu kashi biyu ban sani ba da Yusi ya koma ko kuma ya bar shi a gidan Hajja nasan dai da wahala ya bar shi a can din saboda makaranta kuma akwai sabo mai yawa a tsakaninsu zamansu a tare zasu debewa juna kewa.''
Wallahi ban zaci abin ya kai haka ba a ganina ban cancanci haka ba a wurinsa idan fa da adalci shima ya so kansa ne idan kullum zai dinga zuwa nan yana komawa yana da ikon yin haka tunda jirgi ne kawai bashi dashi amma yana da kudi kuma yana da alfarma a ko'ina,idan ya so duka karshen wata zai iya zuwa ya yi mana sati daya ya koma.
wasa wasa dai yau kwanaki goma kenan da komawarsa bai kira ni a waya ba kuma bai amsa kira na ba.
Abin ya fara damuna wannan ai kin gaskiya ne da gangan!

E mana son rai da gangan domin kowaye ya ji wannan batun ya san son zuciya ne. Sai kawai na rabu dashi dama sautari idan yana irin wannan fushin na bashi ha'kuri ya ki ji share shi nake yi domin daga zarar ya fahimci damuwata akan abinda yake yi sai ya sake  tsanantawa daga na watsar dashi sai kuma ya fara neman shiri.
Sabgarsa na fita saboda na tabbatar da cewa ban yi abinda ya kai ayi mini irin wannan wulakancin ba.
Sati guda ban neme shi ba  ranar litinin da misalin uku da rabi na rana ya kira waya lokacin ma tana hannun Yusura tana game ta kawo mini.
Babu damuwar komai na gaishe shi cikin nutsuwa domin idan na nuna masa na ji ciwon abinda ya yi mini  zai ji dad'i tunda haka yake so   ashe daliline ya sanya shi kirana ba wai ya kira ni domin ya ji yaya nake ba. Kanin mahaifin Hauwa ne ya rasu shine za a yi ayari har da Hajja gobe zuwa can bauchi shine yake ba ni umarinin na shirya gobe da wuri direban gidan Hajja zai zo ya d'auke ni mu tafi tare tunda ni nan bai ajiye mini direba ba sai dai gidan cike yake da masu tsaro.
Jin gaisuwar mutawa ce ya sanya ban yi jayayya ba na ce masa to kawai bai kuma jirayi komai daga gare ni ba ya datse wayarsa cikin raina na ce za ka yi ka gama.
Ina zaune Ina zullumi yadda zan shiga cikin dangin Hauwa da wane irin ido zan dube su domin dai Hauwa ce tasu ba ni ba, bai zama lallai su fahimci hakkina ba tunda itace 'yar uwarsu.

Idan kuma na ce ba zan je ba zai iya zama gagarimin lefi ta yadda za a kama ni da hujja a ce ni ce ba ni son zaman lafiya da Hauwa.
A daran na kira anti Yagana na gaya mata ta yi mini fatan alheri na sanar da Babarmu ma shima dai addu'ar zuwa lafiya da dawowa lafiya ya yi mana

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Da safe da wuri muka shirya don ba mu kai ga karyawa ba ma direban ya iso haka muka tafi da abin karin can gidan hajjan idan mun je sai mu karya kafin mu tafi.
Ban samu wata tar'ba muhimmiya daga wurin Hajja ba, babu wannan k'aunar da nake ganinta a cikin idonta, babu dai k'yama kuma babu sakin fuska muka gaisa kadaran kadahan. B'angaran Hajiya Saratu babu wata matsala sai ma rashin jin dadin abinda Hajja ta yi ya bayyana a fuskarta. Ban nuna damuwata a sarari ba na danneta dama na riga nasan duk daran dadewa inna Uwani sai ta farraka tsakanina da Hajja tunda a zahiri ta fito ta nuna kishin hakan, amma ni a ganina abinda na yi bai kai ace kowa ya kasa yi mini uzuri ba sai dama idan da wata a kasa. Na ji dad'i da ban ajiye ba balle na yi fargabar wata matsala ta kutsu ta rabuwa na yi danasani zan kuma kiyaye faruwar hakan tunda dama da soyayyar Hajja nake gadara an shiga tsakani.
Koda Hauwa ta fito a kintse cikin shiri har da yar k'aramar akwati ni kam ban yi guzurin komai ba sai a lokacin ma na tuna za mu iya kwana fa tunda gidansu ne bai zai yiwu ace mu je mu dawo a ranar ba.
Babu yabo babu fallasa muka gaisa tana zauna kujerar da Hajja ta tashi tana duba wayarta na dinga nazarinta a fakaice ta kara haske ainun abinka dama da farar fata ya yi bul-bul irin na mace mai yaron ciki duk wannan ramar babu ita kirjinta ya ciko  sosai kamar wadda take rayuwa a ketare. Na d'an janye idona a hankali na sauke ajiyar zuciya Ina nazarin yadda za ta kaya domin dai ni ba zan ce direba ya mayar da ni domin d'auko kaya ba idan kwanan ya zama dole na nemi shop na sayi koda abaya ce.
Zaman mota ya sanya kafafun Hajja yin tsami da kyar ta fito daga motar tana kukan kafafunta na yi mata zugi.
Ni na taimaka mata muka shiga gidan Hajiya Saratu da ita Hauwan suna bayanmu Yusura kuma tana gefena ri'ke da jakata a hannunta.
To an ce duk inda mai kudi yake yana da wani irin kwarjini da haiba abinda ya faru kenan saukarmu a gidan rasuwar ke da wuya maza daga waje suka dinga shigowa suna gaishe da Hajja ni kaina wasu daga cikin dangin Hauwa sun mutuntani gaisuwa ta mutunci muka dinga yi da su. wad'anda na fahimci kuma ban ishe su kallo ba ni ma bana kallonsu amma na yi kokarin samun inna Uwani a gefe na gaisheta domin sai satar kallona take yi  kuma ba ta ce mini komai ba. Ta amsa babu yabo babu fallasa sai na  ja gefe guda na kame kaina Yusura na gefena don ma Allah Ya yi mini kwarjini da haiba da ban san abinda zai faru ba. Akwai wasu dana lura suna ta shige da fice a d'akin da aka sauke mu kuma na fahimci sa'anin  Hauwa ne irin 'yan uwan nan da aka tashi tare daya dai daga cikinsu da ta gaza ha'kuri ta dube ni da dan

murmushi irin na munafurci sai ta kalli Hauwa dake kwance lakadan tana lasar lemon tsami saboda yawun da yake cika mata baki tana tambayarta wai Yusura 'yata ce dan an ce dama ina da yara biyu.
Sai ta bata amsa da cewa itama bata sani ba.
Hajiya Saratu da ta fahimci kamar da cin fuska ta yi tambayar ta ce." Sadiya idan 'yarta sai me, ina ce kema kina da 'yan matan yaran nan don Allah ku dinga yin shiru dangane da abinda bai shafeku ba."
Ta na dariya ta ce." Anti Saratu daga tambaya sai a yi mini fassara ayi ha'kuri to."
Ta d'auki wani fulas da yake cike da funkaso ta fice daga dakin.
Hajja ta dan dube ni a nutse ta ce." Wai ni Amina yarinyar wacece ne wannan?"
Na ce." Yarinyar Sahura ce Hajja ai ta jima a hannuna tun tana kan'kanuwa."
Ta ce." Ayya, ai shi Yusi ya'ki zaman nan fafur da Baban nasa zai tafi har da kuka sai ya bishi Shima ya daure masa gindi wai saboda makaranta.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*53*
Murmushi na yi a hankali na ce." Ni kaina Hajja na manta yaushe rabon da naga Yusi ko gidan da na tare fa bai zo ba."
Ta ce." Ai duk lefinku ne kun yi abu a 'kunshe waye zai san halin da kuke ciki, ina sane ni ma ban zo ba, da ya yi mini jagora na duba Gwaggo na yi dawowata gida.."
Da mamaki a tare da ni na ce." Hajja Yusi ne ya yi mini jagora har gidan Gwaggo."
'"Kwarai kuwa shi da direbana kafin su tafi shima baban nasa sai labari ya ji mun je mun dawo."
Na yi kasa da kaina cikin jin nauyi na ce." Ki yi hakuri Hajja hakan ba zata sake faruwa ba in sha Allahu rabbi.
Shiru ta yi ba tace komai ba. Hajiya Saratu kuwa sai murmushi take yi ta ji dadin yadda Hajjan ta saki fuska har muna hira wannan yana nuna mini ko da asirin har yanzu akwai sauran kaunta a cikin zuciyarta.

Sai bayan ishai tukkuna muka tafi gidan inna Uwani dalili gidan da akayi rasuwar a cike yake da jama'a kasancewar gobe ne za a yi addu'ar sadakar uku. Babu nisa a tsakanin gidan mutuwar da gidansu Hauwa gabad'aya muka nufi can din har da ita.

Hajja ta ce gobe da wuri idan an yi addu'a sai mu kama hanya mu tafi gida sosai na ji dadin hakan don haka inna Uwani tana shigowa tana gaya mata abinda ta yanke ta nuna rashin jin dadinta akan hakan har dai ta gaza yin shiru tana gaya mata ita me yasa idan ta je mata take wata da watanni ina lefin ma mu yi sati daya sai mu tafi.
Jin abinda ta ce ya sanya mini fargaba don gaskiya bana so ko kwana daya mu kara a garin bayan wanda Hajjan ta yanke.
Yanayin yadda inna Uwani ta nuna b'acin ranta ya sanya hajjan ta ce idan an yi addu'ar gobe jibi sai mu tafi lokacin dai duk wanda ya kamata a gaisa dashi an gaisa.
Dukda hakan dai inna uwani ba ta ji dad'i ba ta so a ce mun zauna mun yi sati guda kamar yadda ta buk'ata.
Jin shawarar da suka yanke ya sanya na fara tunanin nemawa kaina mafita dole gobe ma mu shiga cikin mutane kuma ba zai yiwu na sake komawa da kayan jikina ba ba don komai ba sai don na siyawa kaina mutunci.
Na gayawa hajiya Saratu abinda yake da akwai da buk'atar son ta yi mini jagora mu fita a daran tunda da sauran lokaci dare bai yi ba.
Hajja ta kama fad'a sosai irin wanda bata taba yi mini ba gabad'aya taki kar'bar uzurina tana fad'in ai nasan ba yadda za a yi mu yi tafiya irin wannan mu je mu dawo a ranar na ce mata mantawa na yi sai da muka fito daga gidan tukkuna Allah ya tunasar da ni. Ina jin inna Uwani da tunda muke maganar ba ta ce komai sai da ta ji hajjan tana yi mini fada tukkuna ta sanyo bakinta wai ko dai ba na son zuwa aka tursasani. Takaici da b'acin rai bai barni na sake wata magana ba, na yi shiru kawai da bakina Ina mamakin yadda yanzu gabad'aya Hajja ta daina fahimtata ta kuma daina tausaya mini. Haka dai muka fita ni da Hajiya Saratu ran mu duka a b'ace domin ita kad'ai ce ta dubi uzurina ta kuma fahimce ni ita Hauwa ma bata iya cewa komai ba har aka yi maganar aka gama kuma tana kwance a wajan amma uffan ba ta ce ba.
Direban da muka zo dashi ne ya fita da mu. Garin ba bak'on Hajiya Saratu ba ne ta san wurare da yawa don haka ma ba mu yi nisa da hawa titi ba muka ci karo da wani shop a d'aya hannun na cewa magaji direba ya shiga damu ciki. Dogwayen riguna na sayo mana ni da Yusura na had'o da hijabai biyu da takalmi flat ko rabin awa ba mu yi ba muka koma gidan Hajiya Saratu tana kara ta tausata don gaskiya yanayinta gabad'aya ya nuna takaicin abinda aka yi mini tana gaya mini ita kanta ta rasa abinda yake damun Hajja a tsukin nan don ta fahimci kamar tana shakkar Inna Uwani dalilin ma da ya sanya ta fara dora zarginta akanta
Na nuna mata babu komai kawai amma can kasan zuciyata abin yayi mini ciwo kawai da gaske, zan yi kokarin ganin na taushi zuciyata har mu tafi wani abu bai faru ta b'angarena ba.
Mussaman aka kunna genareto saboda mu. Gidansu Hauwa sai na ce da kadan ya dara namu gidan kwaryar sama ce take dukan ta kasa. Gidan kuma na had'aka ne mutum uku ne amma kowa da nasa bangaran wanda ya rasu ne kawai gidansa a waje. Mahaifinsu ya rasu kuma shine babbansu sai dai gabad'ayansu 'yan boko ne babu wani dan kasuwa a ciki suna ci da biro da

takarda rufin asiri na abinci ne kawai kuma a cikin sa'aninta dai Ina ganin ita kad'ai ce take auran mawadaci sauran duk sai a hankali suna kula da kansu ne dalilin aikin gwamnati da suke yi sai dai yadda na lura suna da hadin kai da k'aunar junansu ba kamar na mu gidan ba.
Wajan goma da rabi har mun kwanta ni da Hajiya Saratu da Yusura muna d'aki daya ita Hajja da 'yar uwarta suna tare Hauwa kuwa ba na ce ga inda take ba tunda ko lokacin da muka dawo ban ganta a falon ba. Muna d'an ta'ba hira kad'an kad'an Hauwa ta shigo da wayarta a hannunta tana fad'in." Har kun kwanta ne?"
A tsanake na dubeta na ce." E wallahi."
Sai ta miko mini waya tana cewa."  Maigidanki ne yake so ya yi magana."
Na yi sakare Ina kallonta yana so ya yi magana da ni bashi da lambata ne?" Abinda zuciyata take tambayata kenan.
Ta sake maimaita maganarta tana cewa'' Wata'kila ya kira layinki bata shiga ba kin san matsalar network, ni dai yanzu ya kira ni ya ce na hada shi dake."
Ban ce komai ba na amshi wayar sai ta juya ta fita ni da Hajiya Saratu muka bi ta da kallo. Ita dai girgiza kanta ta yi a hankali ta koma ta kwanta ni kuwa na tashi zaune da wayar a hannuna ina tsammanin kiran nasa.
Minti biyar da fitarta ya kira. Na daga a nutse na ji yana cewa." Kin kai mata wayar?"
"Eh ta kawo mini barka da dare?"
Na fad'a tare da ko'karin danne damuwata."
Ya d'an diririce ban san dalili ba can kuma na ji ya amsa yana cewa." Dazu na kira Hauwa a waya ta ce mini kun fita ke da Hajiya Saratu ina kuka je?"
Babu mamaki a tare da ni saboda nasan zai iya yin abinda yafi haka  na furta." Ta yi mini rakiya ne na sayo abu a shop saboda ban yi guzurin kaya ba don  ban yi zaton zamu kwana ba."
Ajiyar zuciyarsa na ji kafin ya ce." Kada ki kara shiga wani shago da zummar sayan kaya Amina hakan yana nufin abubuwa da yawa, kin san dai ba zai yiwu ace ku je bauchi ko dawo a ranar daya ba, me yasa ba ki bawa maganata muhimmanci ba a lokacin dana kira ki na gaya miki ki shirya ki bi su."
Na hasala da jin yadda yake  ko'karin d'ora mini lefi shekkenan ni ba zan yi kuskure ba, kuma ai da ya gaya mini bai ce mini na hada kayana kwana za mu yi ba."
Na ce." Shine me? ai lefin ba na kowa ba ne naka ne ko ka gaya mini na hada kaya zamu kwana? da ka kira ni ka sanar da ni na bijire maka ne, na ce to shikkenan ban yi maka jayayya ba saboda kuskure karami sai kuma a gaza fahimtata."
"Ban kira ki don ki gaya mini magana ba Amina, na ce kada ki sake shiga shago ki ce za ki sayi abu ina da dalilina."
Shiru na yi ban ce masa komai ba sakamakon yadda na ga Hajiya Saratu ta tashi zaune tana kallona da yanayi na damuwa.
Sai kawai na datse kiran ban tsaya na saurari sauran maganarsa ba, wane irin dalili ne dashi wanda ya wuce na tozarci shikkenan don ina a matsayin na matarsa ba zan shiga shago na sayi abu ba ni din wacece. Itama Hauwa

ta so faruwar hakan hakan ne amma menene na gaya masa ga inda muka tafi bai kira ni a waya don ya nuna ya ji dadin karar da na yi musu ba ya kira ni yana tuhumata akan wane dalili.
Ban iya daure kukan da yake ta yun'kuro mini ba na fara share hawayen da yake gudana a kumatuna Yusura ta yi lamo akan katifa tana kallona kamar ta taya ni kuka.

Wannan littafin na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Hajiya Saratu ta dafa kafadata tana rarrashina a yanzu ita kadai ce take nuna damuwarta a kaina Hajja kam sai a hankali 'yar uwarta ta samu galaba akanta.
Hauwa ta shigo domin ta kar'bi wayarta ta same ni Ina kuka muna tattauna abinda yake faruwa da Hajiya Saratu sai ta yi kasa'ke tana kallonmu a lokacin Hajiya Saratu ta rufe ta da fad'a tana cewa." Ki ji tsoron Allah Hauwa yadda ki ke ko'karin gyara auranki to na hore ki ki gyara na 'yar uwarki wadda ki ka zo ki ka sameta da mijinta, bayan abinda ku ke yi na karkashin kasa har sai kin yi mata bita da kulli kin san fa duk abinda ya faru me zai sanya don ya kira ki a waya sai ki gaya masa shikkenan mutum baya kuskure..
Babu wata damuwa a tare da ita ta ce." Sai na yi karya kenan ko anti Saratu na ce masa gata nan a kusa da ni ko me? Ya tambayeni ina take na ce masa kun fita tare zata sayo kaya ko ba haka na ji kuna maganar ba. A lokacin da na yi masa karya ya ce na bashi ita kuma na yi yaya kenan, kuma na ji kina cewa muna yin abu ta k'arkashin kasa, ita din da kike shedarta kina da tabbacin ba ta yi ne? ai alhaki koikoyone wata'kila abinda ta yi ne ya waiwaiyo mata, ni wannan ai sai dai na kalleta kawai 'kiri-'kiri tana nuna mini 'kyama ta kuma fito da hassada da kishinta muraran a kaina ciki dai da izinin Allah sai na haifehe ko ana so ko ba a so gwara ma mutum ya ha'kura ya barwa Allah ikonsa

Maganganun Hauwa sun yi mini nuni da cewa tabbas ta ji ciwon abinda na yi wanda har hakan ya sanya suka hade mini kai ita da mijinta. Amma kuma sun yi tsauri ga hajiya Saratu wata'kila ko ta manta da cewa ita din yayar mijinta ce fa ba kanwarsa ba, a tunanina ko kanwarsa girma da shekarunta bai kai ace ta tsaya a kanta da fitsara.
Ni idan ta yi mini kishiyarta ce ba abin damuwa ba ne tunda da kishi a tsakaninmu amma ni da ban had'a jini dasu ba ba zan ta'ba yi wa mai shekaru irin na Hajiya Saratu rashin kunya ba.

Abinda ya haddasa musu rikici kenan a tsakaninsu sai ya zamana ni na shiga tsakiya kuma a ta dalilina komai ya faru Hajiya Saratu fadi take yi "Ba za ta je ta zauna miki ba din, ko ita ce ta yi miki cikin, ai ni Amina ta yi mini daidai duk abinda za ku ce akanta kun dade baku fad'a shegiya mara kunya ki dubi tsabar idona ki dinga nema ki zage ni saboda kin samu kanki ko, idan kin

manta bari na tuna miki ni Yaya nake ga Tajo ba k'anwa ba balle ki ce za ki gaya mini magana son ranki Ubanki zan ci domin ba na ciki da iskancinki shashasha mara wayo kawai, ai iliminki bai amfana miki komai ba sai rashin dubara......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*55*
Sai zamanta ya rage mini kad'aici mussaman idan Yusura ta tafi islamiyyar dana sanyata anan bakin titi domin ta cigaba da dora haddarta kasancewar dama ta yi saukar al'kur'ani wattanin shida da suka wuce wanda ya yi daidai da lokacin da ta zana jarrabawar fita daga secondary da kaina na yi tunanin sanyata a makarantar saboda zaman a haka bashi da amfani zata sake d'aukar darrusa masu muhimmanci kafin lokacin auranta tunda makarantar ba wai al'kur'ani kawai suke koyarwa ba har da sauran littafain na addini za ta kara sanin tsarki da hukunce-hukuncensu.

Ranar da Sahura ta zo yini muka yi muna magana daya har dai na gaji na yi mata shiru domin kuwa ba zan ta'ba yin abinda take so ba don ban ga abinda na yi ba ai na d'auka sai mutum ya yi lefi tukkuna zai ta bibiyar wanda ya yi wa domin ya yafe masa.
Ita kanta tasan maganata akan daidai take ba zai yiwu ace sun mori juna sun jiyar da kansu dadi  ciki ya samu ace ni kuma dake gefe na je na yi musu wahala ba, ai ba yarinya ba ce balle ace kuma ita din menene bata sani ba tunda malamar asibiti ce duk wanda zai zage ni ya dad'e bai yi ba abu ne mai mutukar wahala wata mace ta aminta da hakan.
Ita Sahura wai kada mutane su yi mini wata fassara ko a juya maganar ace ina yi mata b'akinciki don ta samu cikin haihuwa wanda ni kuma wallahi babu wannan a cikin raina komawa ne kawai ba zan yi ba, ni ma a lokacin da na samu nawa haka nayi ta fama dalilin ma da ya sanya kenan nake d'agawa Hadiza kafa saboda wahalar da ta yi mini.

Wai lallai sai na kira shi na bashi ha'kuri na gaya mata ha'kuri kuma na nawa lamarin da ba yau akayi shi ba an kusa wata biyu to me zai sanya na damu kaina. Ina nan dai da kudirina wata uku na cika idan bai zo ba to kuwa zan san inda dare ya yi mini ai ko addini wannan abin da yayi ba daidai ba ne kuma daf yake da ya lalata auransa.

Duk hujjar da ta kawo mini zan soke ta dole sai ta ha'kura ta kyaleni ta tafi da b'acin rai dalilin da na ki na yi abinda take so.
Babanmu da Baba Sule suka zo ranar wata jumaa bayan an sakko daga massalaci na ji dadin zuwansu sosai na shirya musu abinci mai kyau suka ci suka koshi suna ta yaba gidan  da fatan alheri na dinga nazarin Baba Sule gabad'aya duk ya susuce tufafin ma dake jikinsa kamar ba wankakke ba takalmi irin soso shine a kafarsa. Babanmu ne kawai cikin sutturar arziki tsaf dashi, sai na ji kunyar hakan a cikin zuciyata ko babu komai Baba Sule uba ne duk lalacewsa kuwa, duk ranar da babu ran Babanmu dole shi din zamu k'alla a matsayin Ubanmu kuma idan da kara duk wata taguwa da zan dinkawa Babanmu shima ya kai ace na had'a dashi ganin da na yi masa babu kintsi ya sanya jikina yin sanyi domin yanayinsa ya nuna yana buk'atar agaji ilai kuwa ashe damuwa ce mai yawa a tattare dashi dalili ubangidan nasa Alhaji Muntari ya karye jinya ta cinye masa kudi ga tarin bashin mutane dake kansa komai ya karye masa wasu sun ha'kura wasu kuma sun ce sai an biya su, wannan dalilin ya sanya gidan da yake ciki aka sanya shi a kasuwa domin biyan bashin da yake kansa. Yadda Baba Sule yake mini bayani lamarin ya bani tsoro mutuka da gaske yanzu uwargidansa anti Maimuna ita kadai ce ke jinyarsa anti Jamila ta gudu garinsu Bichi bayan ta turasashi ya saketa wai ba zata iya zama ta lalata kuruciyarta a banza ba. Yana gaya mini baban yaronsa namiji wato Turmuzi yana nan yawo cikin tashar Kano line yana bin 'yan kamasho da samarwa da matafiya mota a sallameshi ya lalace da shaye-shaye tunda wasu lukutan a tashar yake kwana sai yayi sati bai je gida ba.
Kuka sosai na dinga yi ina kiran sunan Allah amma anti Jamila ba ta yi wa kanta adalci ba, ni a tsarina duk wahala ba zan iya watsar da yarana akan jin dadin duniya ba, babu ma yadda za a yi na tafi na bar yarana a wurin da nasan ba zasu samu kulawa ba hankalina ma ba zai ta'ba kwanciya ba. Anti Maimuna ta ba ni tausayi sosai ita kuma tata jarabawar kenan rayuwa kenan. Ba ni da halin da zan iya biyawa Alhaji Muntari bashi har na kusan miliyan talatin gabad'aya ma abinda nake juyawa bai kai hamsin ba ribar da take fita yau da gobe da ita muke buk'ata ni da Hamusu da kuma biyan yaran shago hakkinsu. Alhaji Tajo shi yake da iko koda miliyan dari ne don ya fitar ya bayar ba na tsammanin dukiyarsa zata girgiza amma da nauyi sosai a ce na tunkare shi da wannan maganar har cikin raina nake jin wani iri dangane da ibtila'in rayuwar da ya faru da Alhaji Muntari domin ko banza ya taimaka mini ni ma a can baya a wannan ga'bar ya kamata ace na tagaza wani abu kafin akai ga kar'bar kudin gidan da yake ciki wannan duniyar ta zama abar tsoro.
Haka na kwana na yini da tunanin hanyar da zan bi wurin ganin na nemi taimako daga wajan wannan wannan d'an tahalikin ba tare da ya fassara ni ba.
Na kira anti Yagana na gaya mata domin ta ba ni shawara itama dai abinda Sahura ta ce shi ta fad'a na sauke abinda nake ji kawai na neme shi domin yin hakan babban taimako ne da zai sanya ni dashi mu tsinta a ranar lahira. Na yi na'am da shawararsu domin a raina na ji zan iya jure cin kashi da bakaken maganganunsa muddin zai taimaka ai me nema baya fushi ni ko

bashin ne ma ya biya masa su dai zauna a gidan ni kuma zan yi kokarin ganin na d'auki nauyin kaishi babban asibiti domin a duba lafiyarsa sosai.
Na samu lokaci ranar lahadi da la'asar domin a irin wannan lokacin ne yake free sosai na kira shi a waya daf da zata katse ya daga yana sallama.
Na amsa a nutse kafin na gaishe ya amsa can kasa kamar wanda yake cikin mayen bacci.
A sanyaye na ce." Dama na kira ka ne kawai na gaisheka na ji ya kuke ina Yusi."
Ya ce." Ina nan lafiya muna nan Abuja tare dashi gidan babban abokina Alhaji Amadu na taba baki labarinsa ko?"
Na ce." Eh kun dai ta'ba yin waya sau daya a gabana ina yawan jin sunansa a bakinka."
A dan sanyaye ya furta." Yana nan rai a hannun Allah Amina yana jin jiki muna kan shirye shiryen tafiya asibitin jiddah nan da kwana uku"
Jikina a mace na ce."inna lillahi me yake damunsa haka?"
"Kin san yana da ciwon zuciya dama to wannan karon da ciwon ya motsa masa abin ba kyau ni har na fara fitar da raina a kansa Amina."
A sanyaye na ce." In sha Allahu zai tashi zai samu lafiya."
Ya ce." To Allah Ya sa, ina fatan dai lafiya kuke na yi mamakin kiran da ki ka yi mini a wannan lokacin da ban yi tsammani ba, ni da kika kullace ni kina gaba da mijinki ko Amina baki damuwa da halin da nake ciki ba, ai ina kallon yadda ake soyayya a wurin Hajiya Maryam mai d'akin abokina Alhaji Amadu amma ni da nake da mata biyu  kun yi watsi da ni ko, ita waccan din idan an yi mata uzuri ke fa? son ranki kike bi, ba ki damu da abinda zai same mu ni da Yusuf  ko ba haka ba ne?"
Jiki babu kuzari na ce." Ban kyauta ba ka yi hakuri amma me yasa ka gaza fahimtata ya kamata ku yi mini adalci a wannan lamari sai ka tsiri gaba da ni, ban kullaceka ba kaine ma kake jin haushina dalilin da ya sanya ma kenan na ga rashin dacewar haka na kira ka yanzu domin mu sasanta gabar ta isheni haka.

"To tunda kin nemi sulhu zuwa za ki yi inda nake ai ki lallaba ni domin ni ma ba ni da wata lafiya rashin lafiyar abokina ta dame ni a kwanakin nan Ina buk'atar mai kula da ni ta ba ni magani ta kuma kwantar mini da hankali da kalamai masu dad'i zuciyata ta daina yi mini tunanin kamar ban yi sa'ar iyali ba."
Cike da mamaki na furta." Yallabai duk me ya kawo wannan maganganun don Allah."
Ya nisa kafin ya sake cewa." Kulawar da abokina yake samun wurin iyalinsa shine ya sanya nake jina kamar maraya gashi dai babu abinda Allah ya rage ni na jin dadin duniya amma matata ta na yi mini wulakanci."
Dariya maganarsa ta ba ni wai wulakanci wato shi baya duba abinda yake yi mini a matsayin wulakanci saboda namiji ne duk abinda ya yi daidai ne."
Na yi dariya 'yar kad'an kafin na ce." To shi ba ka ganin bashi da lafiya ai dole a ninka bashi kulawa ko ka manta lokacin da ka yi mura a gidana yadda na dinga lalla'baka ina rarrashinka kamar jariri."

Ya ce." Ni dai na gaya miki zan sanya a kawo miki ticket da za ki same ni anan abuja gobe kafin mu wuce saudiya ki ba ni magani kada na tafi da lalura.
A dukunkune yake maganar amma na gama fahimtar inda ya dosa wannan ya nuna mini cewa a mutukar bukace yake dauriya ce kawai da son dole sai an nuna iko ba zai neme ni ba muddin ba ni na neme shi ba yanzu kuwa dana tsaga billena na kira shi kai tsaye yake neman abu a wurina.
Ni ma saboda tawa biyan buk'atar yasa babu ja'inja na amshi gayyatarsa nasan ta wannan hanyar zan iya samun abinda nake so kai tsaye tunda Allah Ya riga ya ga zuciyata da munufaar da zanyi hakan.

Daya daga cikin masu yi masa jigila
ya turo da mota ya d'auke ni sunan shi Ade wani bayerabe mai gaggausan jiki da rashin fara'a
bayan saukata a garin abuja kai tsaye gidanshi da yake maitama ya nufa da ni kamar yadda ya bada umarni sai dai da yake ya san matsayina duk cud'ewar fuskarsa bai hana shi risina mini ba.
Gidan kwatankwacin na Legos me d'auke da bangarori da dama kuma cike da ma'aikata da masu tsaro da iyayen motacin da na tabbatar da cewa wasu ma sai a yi shekara ba a hau su ba.
Wurin ajiye motoci ya nufa domin gyara parking yayin da nake hangen maigidan da Yusi can daga nesa bakin wata bukka irin ta hutawa.
Yana kashe motar ya fito da sauri ya bude mini kofa har yana dan risinawa na fito a hankali Yusi ya taho a guje ya rukunkume ni yana dariya mamaki mai yawa ya lullubeni ganin yadda yaron ya yi wata iriyar ki'ba kamar wanda aka hura ya zama kato Na dinga binsa da kallo irin na mamaki da al'ajabi wannan wace irin ki'ba ce. Maigidan ya k'araso wurin yana sanye da jallabiya fara mai karamin hannu kansa da fara hula irin ta larabawa as'usul idonsa da farin gilashinsa. Na dube shi na 'yan dakika na fahimci zurmawarsa ya kara tsukewa dama abinka da mai karamin jiki ko dai da gaske yake shima din bashi da lafiya....✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*56*
Ade ya fito da k'aramar akwatina da na zubo kayana kala uku a ciki ya tsaya suna magana ni da Yusi muna gefa ya rike hannuna gam a cikin nasa yana

cike da tsananin farinciki  ni kam kallonsa kawai nake yi har na gaza ha'kuri na ce." Kai me ka samu ka ke ci ka zama d'an lukuti kana duba mudubi kuwa?"
Dariya ya kama yi yana cewa." Abinci kawai nake ci ai an yi hutu makaranta Mama amma ina hawa gym na tsinka jina na."
Na dube shi a lokacin da ya zo ya tsaya gabanmu Yana cewa." Ke kuma daga zuwa sai tuhuma."
Yar dariya na yi a hankali na ce." Abin ne ai da mamaki wallahi kibar ta yi yawa." Ya wuce ciki yana cewa." Ke ki ka gada masa ai ba kowa ba.''
Yusi ya kamo hannuna muka bi bayansa yana ta yi mini labari yaran Alhaji Amadu wanda suka zama abokansa jinsa kawai nake yi amma ban ce komai ba sai dai zuciyata cike take da farincikin ganinsa cikin walwala da kyawun yanayi tare da lafiya da suttura irin ta 'ya'yan manya a jikinsa.
Ga gida har gida babu abinda babu a ciki ko 'diyar shugaban kasa za a iya ajiyeta a gidan amma kash babu mace a cikinsa asalima ya tanadi gidan ne kawai domin idan ya zo garin ya sauka a cikinsa tunda karfin zamansa ya fi legos.
Ya d'an ba ni tausayi kad'an domin kamar yadda ya fad'a cewa Allah bai tauyeshi da komai ba na jin dad'in duniya sai  ta bangaran iyali, Ina ganin da zamansa anan yake dindindin zan iya ha'kura da can na zauna tare dashi to karfin zamansa ba anan yake ba, ni kuma gabad'aya zaman legos din ne ya fice mini daga raina.
Wajan cin abinci cike yake da cima kala kala da kayan marmarin dogon daning ne mai d'auke da kujeru takwas gaba da baya tsarin gidan gwanin ban sha'awa kuma a gare cikin tsabta kasancewar akwai masu aiki maza da suke yi hidima a gidan koda baya nan.
Sama ya hau nan turarkarsa take Ade ya shigo da akwatina ya ajiye ya fita, Yusi ya tashi da sauri ya bi bayan shi yana kiran sunan shi na bi yaron da kallo da alama akwai sabo a tsakaninsu.
Ajiyar zuciya na sauke a nutse nake bin falon da kallo ya tsaru ainun ya ji kujeru da labuleye na alfarma hotonsa dana iyayensa gasu nan birjik a falo can na hangi na baby Nana kato a wata kusurwa a jingine ba a kafe shi a bango ba.
Na jima tsaye ina duba hoton na share kwallar da ta ciko a idona na d'auka a gidansa na legos kadai ya ajiye hotonta ashe yana dashi a nan d'in ma.
Yana ba ni tausayi sosai a wasu lukutan domin shi din abun tausayi ne....
Sai da na d'an samu nutsuwa tukkuna na tashi na hau saman tunda nan naga ya nufa ai  nasan wulakanci da shan kamshi zansha shi nasan sai dai na kai zuciyata nesa.
D'akuna hud'u ne kowanne a rufe sai guda daya da naka key a jikinsa ta waje hakan ya tabbatar mini da cewa yana cike ina ta'ba kofar kuwa ta bude na shiga da sallama a bakina.
Ya fito daga bandaki daidai lokacin da na shiga d'akin wanka ya yi ya ce." Shigo ciki sosai mana."
Na kàrasa na zauna gefan gado ina dubansa da gaske fa ya rame yanzu na sake gazgatawa da babu riga a jikinsa sa towol da ya dauro.

Ya dube ni yayin da yake ko'karin zama kusa da ni yana fad'in." Ya gajiya?"
Na daure a hankali na ce." Alhamdulillahi ya jiki ashe da gaske dai ba ka da lafiya Baba."
Ya ce." Lafiyata lau me ki ka gani?"
Kai tsaye na ce." Ramewa na ga ka yi?''
"Fargaba ce kawai wallahi na jima ban ga ciwon da ya tayar mini da hankali kamar na Alhaji Amadu ba sam ya'ki jin magani, yana nan fa sai dai a kwantar a tayar na gaya miki yana asibiti a yanzu amma jibi za a yi masa transfer zuwa asibitin makka.
Cike da alhini na ce." In sha Allahu zai samu lafiya kaima ya kamata ka cire damuwa daga ranka kada wani ciwo ya sameka ka rame fa sosai Baba dama kai ba jiki ba."
Yana yi mini wani irin kallo ya ce."Abin har da zolaya Amina."
Girgiza kaina na yi a hankali na ce." Ban isa ba, kawai dai ramar taka ce ta d'an tsorata ni Yusi kuwa kamar wanda ake hurawa."
Ai irin jikinki ne dashi na gaya miki ke ce ki ka gada masa 'kiba.
Ya tashi ya nufi wardrobe yana fito da kayan da zai sanya ya ce." Da daddare idan kin huta za mu je ki duba shi ko?"
Na ce." In sha Allahu rabbi." D'akin ya yi shiru na mintina shi yana ta hidimar shirya jikinsa yayin da ni kuma nake bin d'akin da kallo karaf idona ya sauka kan dirowar dake gefan gadonsa karamin hoton Samira ne irin wanda ya ajiye a gidansa na legos wanda na sanya ya cire shi.
Kishi na ji ya soke ni, ai ta riga ta mutu shekara da shekaru ya kamata ace yanzu ya cire ta a ransa amma ace kowane gidansa da hotonta a ajiye ban san menene amfanin hakan ba.
Ya juyo yana kallona ni kuma na janye idona daga kan hotonta ina ko'karin danne abinda nake ji.
Bai ce mini komai ba ya zauna gefan gadon tare da gyara zaman hoton dukda ba abinda ya yi ganin haka ya sanya na tashi tsaye sai ya yi saurin fad'in." Ki yi wanka sai mu sauka mu ci abinci ko?"
Ban ce komai ba na nufi bandakin zuciyata babu dad'i hotonmu ya fi kamata a ce ya ajiye gefan gadonsa ba na wadda bata raye ba, na fahimci har yanzu akwai sonta a cikin zuciyarsa hirarta ne kawai ba ya yi mini tunda ya fahimci ba na so.
Muna cin abinci yake gaya mini Yusi a gidan abokin nasa yake kwana tare da yaranshi da yake matarsa daya Hajiya Maryam auran saurayi da budurwa suka yi kuma da yake 'yan boko ne sun tsara rayuwarsu haihuwa uku sukayi suka dakata sun fara da mace  mai suna Nusaiba  wadda suka aurar da ita shekara biyu da ta wuce anan abujan tana auran babban ma'aikaci a central bank. Sai kuma Salim wanda yanzu yake matakin shekara ashirin Adam kuma sha bakwai.
Hajiya Maryam yar boko ce  kuma muguwar 'yar gayu ce irin matan nan ne masu kyawun jiki da ado da kwalliya shekarunta sun buya sosai idan ka kalleta sai ka d'auka bata fi talatin ba amma ba haka ba ne shekarunta arba'in da d'aya a yanzu tsabar gyaran jiki ya sanya komai nata yana nan cif

mussaman kirjinta sai da basu da wani girma amma dai tana kula da jikinta ainun.

kuma yar kasuwa ce domin manyan shop ne da ita garin abuja da kano da kuma reshenta a jos tunda asali nan ne mahaifarta amma dai harkokinta sun fi yawa a Abuja tana fita kasashen larabawa mussaman dubai da Qatar da India domin sarin kaya dogwayen riguna takalma sari irin na indiya da kayan maza Pakistani da kuma bangaran sarkoki abin hannu agoguna da sauransu. Yar kasuwa ce sosai wadda arzikin mijinta bai sanya ta nemi wuri ta zauna ba. Da yana gaya mini Yusi ya sha'ku da yaranta dalilin gidajensu na ma'kotaka da juna ban yi mamaki ba domin na tabbatar da cewa Yusi zai iya zama da kowa saboda yana da hankali da kuma iya mu'amula shi ma kuma Allah ya sanya masa kwarjini da farinjini a duk inda ya shiga.

Bayan Isha'i ya d'auke ni a mota da kansa ya yi direving din motar muka nufi asibiti a can muka samu Yusi tare da matasan yaran suna zaune kusa da gadon da mahaifin nasu yake kwance ko'ina na jikinsa sa'kale da na'ura yana ta kokawa da numfashi

Gaskiya dan adam ba abakin komai yake ba idan ma kana d'aukar kanka kai wata tsiyane wallahi gwara ka yi karatun ta nutsu domin Allah ne mai sarrafa al'amura gashi dai da kudin wanda da yawa muke ganin kamar sune karshen jin dadi bayan ba haka ba ne mai lafiya shine d'an gata domin kuwa duk wanda Allah ya wadata da lafiya shi ya yi wa arziki..

Ita da yaranta sun ba ni tausayi kwarai da aniya kuma yanzu na sake gazgata maganar da ya yi mini jiya a waya cewa suna mugun tsananin son junansu shiyasa gabad'aya ta susuce! Ta kasance kullum cikin zubar da hawaye...Da kyar ta iya amsa gaisuwata hankalina gabad'aya na kan maigidan nata da ko yatsansa baya motsi shi kansa na lura da kid'imewarsa da likita ya shigo suna magana yake tambayarsa ya ga an sake sanya masa oxygen bayan jiya aka cire ta kuma numfashinsa ya daidaita likitan ya ce masa ciwon ne ya sake tashi d'azu da yamma amma kuma numfashin ya fara daidaita ba kamar d'azu ba. Ya sake duba shi ya fita shi ma da yake likita jikinsa a mace balle ga mu da muke zaune.

Sai wajan goma da wani abin muka bar asibitin cikin damuwa da zullumi domin kukan da Hajiya maryam din take yi ya ta ba mu gabad'aya har dashi gabad'aya yanayinsa ya canza shi bai yi na hawaye ba yana na zucci irin mai mugun cin ran nan.

Na d'auka damuwar da yake cike ba zata bari ya nemi wata buk'ata ba. A daran bai iya bacci ba sai da ya kwanta da ni irin kwanciyar da na ji jiki a hannunsa har abin ya fara ba ni tsoro ganin yadda ya 'kirkiro wani style wanda ba mu ta'ba yin irinsa ba. Ban fahimci komai ba sai wahala saboda bai jima yana yi mini wassanin soyayya ba ya fara gudanar da abinda ya kud'irce a cikin ransa wanda tun ina yi masa kawaici har dai na gaza ha'kuri na gaya masa fa bana gane komai sai zafi da ciwon cinya. Ya ce shi kuwa atafau ta haka yake so ya yi don ya fi jin dadi. Haka nan na ha'kura na kyaleshi ya dingi yi tamkar wani sabon angon da ya jima yana shan sassa'ke. Wallahi kasa juriya na yi don duk fitinata wannan lamarin ya sha kaina kamar da zalinci a ciki. Ashe lumbu lumbu ya yi mini na zo hannu ya yi mini 'keta kuka

kariris na dinga domin ya rabu da ni yana fad'in bai gama ba tukkuna. Da ya gama kuwa sai da na yi ruwan d'umi sannan na ji sasaauci na nemi waje can nesa dashi na kwanta cinyoyina suna ta ciwo. Na jima kafin bacci ya kwashe ni ina ta kallonsa yana baccinsa hankalinsa a kwance.
Can gefin asubahi kiran da ya shigo wayarsa ya tashe mu gabad'aya a zabure ya lalubi wayar yana dubawa da sauri yasa a kunnansa yana fad'in." Alhaji Jamil....."Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wannan kalmar ce ta fito daga bakinsa bayan ya gama sauraran maganar mai kiran wayar wanda na ji ya kira shi da Alhaji Jamil.

Dama a wasu lukutan mutuwa takan nuna kama kafin wa'adin ya cika. Ni dai dama ganin da na yi wa Alhaji Amadu a wannan dare na sare domin gwiwata a sanyaye muka fito daga asibitin lokaci kawai yake jira amma alamun sallama da duniya ya gama bayyana a tattare dashi. Alhaji Jamil k'anine ga Alhaji Amadu tare suke ta tiriri dashi shi k'aninsa ne uwa daya uba daya shi kuma abokinsa ne tun na 'kuruciya abokin da akayi gwagwarmayar rayuwa.
Mutuwar Alhaji Amadu ta dake shi mutuka gaya domin ni sai na ce tunda na tashi daga kuruciya da girma ban ta'ba ganin kukan  babban mutum  kariris irin haka ba.
Na fahimci ya yi kokari sosai wurin ganin ya danne kukan amma hakan bai samu ba  kuka ya dinga yi sosai amma ba mai gunji ba yana nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! lamarin ya tsoratani sosai wanda hakan ya sanya ni ni ma fashewa da kukan domin na rasa yadda zanyi na rarrashe shi.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*57*
Shine akan gaba wajan shirya Alhaji Amadu har aka kaishi gidansa na gaskiya, haka ya dinga kai kawo har ya ba ni tausayin da na ji kwalla ta cika kwarmin idona. Tabbas Alhaji Amadu ya wuce aboki a wurinsa sai da d'an uwa, domin tun a daran kafin gari ya waye ya dinga gaya mini irin gwagwarmayar da suka sha duk domin tsayuwa da kafafuwansu. Marigayin ya riga shi auran fari kusan shine ma ya yi masa rakiya ta angonci kuma tare suka dinga jigilar zuwa jos neman auran Maryam din har  dai Allah Ya tabbatar da auran. Shekaru kusan goma sha biyu da auransu ne shi kuma ya yi auran fari Samira kenan Allah kuma ya dinga wanzar da ikonsa.

Ni kam da babu sha'kuwa a tsakanina da Hajiya Maryam ban nuna bak'untata ba mijina abokin mijinta ne sannan yarona yana tare da nata yaran ta ri'ke gabad'aya dalilin da ya sanya kenan na shiga cikin 'yan uwanta na zauna tare dasu har dare muna kar'bar gaisuwa a tare. Na sake yin karatun duniya sosai domin mutuwa wa'azi ce ga duk wani mumini na kuma tausaya mata kwarai da aniya ganin yadda ta zabge ta ki'dime a lokaci d'aya babu shakka mutuwar miji wani babban rashi ne da har abada ba za a ta'ba maye gurbinsa ba.
Sai wajan tara da arba'in tukkuna na shiga gida tunda muna kusa da juna amma ban tafi ba tukkuna sai da na tabbatar da cewa ta ci abinci domin yini guda babu abinda yake cikinta babu irin rarrashin da ban bakin da ba a yi mata ba tace ba zata iya cin komai ba. Itace babba a cikin 'yan uwanta shiyasa da suka gaji da rarrashinta suka ha'kura dalili duk ta girmesu iyayensu kuma basa raye itace ke ri'ke da ragamarsu gabad'aya ni ma na tabbata don tana jin kunyata ya sanya ta kar'bi abincin da na hada mata da hannuna ta dinga ci kamar magani tana goge hawayen da suka ki daina fita daga idonta.
Bai shigo ba sai wajan sha biyu saura shi Yusi yana can dama lokacin da ya shigo din har na yi shirin kwanciya amma ban kwanta ba din tukkuna ina dakkon shigowarsa.

Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Wanka ya fara yi tukkuna ya same ni a zaune a gefan gado ya zauna kusa da ni. A nutse nake dubansa gabad'aya bashi da kuzari na ce." Sannu baba ya karin ha'kuri?"
Ya amsa da "Alhamdulillahi yana dan duba wayarsa ya ce." Gobe su Hajja suna tafe tare da Hajiya Saratu da sauran 'yan uwan mahaifina."
Na ce." Ubangiji Allah ya kawo su lafiya amma ka ci abinci kuwa?"
A nutse ya ce" Na ci amma ba mai yawa ba."
"Ko kana buk'atar wani abu yanzu wanda sai sanya cikinka ya dan yi nauyi."
"Wannan towon naki nake sha'awar ci irin wanda ki ka yi mini a gidanki amma dare ya yi yanzu za mu bari da safe sai ki yi mini ko?"
Cike da kulawa na ce." Muddin da akwai duk abun bu'kata yanzu ma sai na yi maka har da d'umame ai ba wani abu ba ne."
Ya girgiza kansa yana yi mini wani irin kallo ya furta." Ba ni da imani sai na sanya ki aiki da wannan dare duba lokaci fa sha biyu har ta gota."
A nutse na ce." To ai aikin lada ne?"
Ya d'an jima yana kallona kafin ya girgiza kansa da cewa." Ki huta kawai na gode."
Jikina ya d'an mutu da yawan kallon da yake yi mini wanda na kasa tantance na menene na soyayya ne ko na wani abin ne.
Wayarsa yake latsawa kafin yasa a kunnansa ban tsammaci da Hauwa yake waya ba sai da na ji yana fad'in." Kin fi kowa sanin matsalar hakan tunda ma'aikaciyar lafiya ce ke to me zai sanya kuma ki aikata, idan kika zubar da

cikin ai mun huta gabad'aya tunda ke ba za ki yi aiki da abinda ki ka sani ba."
Ban ji abinda take ce masa ba. Ya ce." Ina cikin jama'a ne sosai muna kar'bar gaisuwa abokin nan nawa Alhaji Amadu ne ya rasu nasan zuwa yanzu kin samu labari ko ta kafafan sadarwa ne dalilin da ya sanya kenan ban samu damar amsa kiranki ba gashi yanzu da na nutsu na kira ki da kaina."
Shiru ya yi yana sauraranta har ta gama yi masa magana cikin kuka wanda nake jin sautinsa kad'an kad'an. Ya ce." To shikkenan a d'aure mahaifar idan hakan shine solution ai kin fi kowa sanin hakan tunda ajikinki take gobe ki je asibiti da wuri ayi miki aikin Allah Ya sawwa'ke."
Ya kashe wayar da damuwa a tare dashi. Ni ma sai na ji hankalina ya tashi wato dai muddin kana raye a duniyar nan ba zaka huta ba.
Bai gaya mini ba amma na fahimci kadan daga cikin abinda suka tattauna cikinta ne yake barazanar zubewa. Na gaza ha'kuri na tambaye shi ya ce." Wai fita suka yi suka yi tare da Sadiya tafiyar kasa mai tsayi saboda rashin hankali tasan tana da karamin ciki bayan sun dawo gida shine take ganin jini kad'an kad'an wai tana tunanin cikin zai iya zubewa dole sai an yi d'aurin mahaifa."
Da damuwa a tare da ni na ce." Aikuwa dai yana da kyau ta yi gaggawa zuwa asibiti gobe wata'kila tana da matsalar mahaifa bata da k'wari shine dalili amma kuma itama ta yi ganganci yin doguwar tafiya a k'afa tana da karamin ciki kamar ba ma'aikaciyar lafiya ba.
Ya ce." Abinda take zargi kenan idan cikin ya zube ai ta huta."
Ya k'arasa maganar cikin takaici da jin haushin lamarin.
Haka kawai na ji na damu da hakan domin har ga Allah bana so wani abu ya samu cikin Hauwa ba don komai ba sai don ganin tabbatuwar farinciki da walwala a fuskarsa. A yanzu dai zuria itace karshen abinda yake nema a wannan duniyar bayan Allah Ya wadatashi da komai a duk lokacin dana kalleshi na tuna har yanzu bai ajiye magaji ba hankalina yana tashi sosai kuma nakan zubar da hawaye masu yawa domin jarabawar da ta same mu ni dashi na riga nasan ko na saki zuciyata da gangar jikina na haihu za mu sanya rai ne akan abinda muka samu bayan kuma ba mai d'orewa ba ne. Astagfirullahi wannan shine babban dalilin da ya sanya nake ji a cikin raina ko cikin na samu zan iya zubar dashi ba tare da ya sani ba don gudun shiga damuwa matsananciya bayan na bari na haihu muna ji muna gani mu rasa abinda muka samu kamar yadda muka rasa babynmu ta farko.
Abin mamaki da daure kai a wannan daran ma na jigatu kwarai da aniya a hannunsa don ban ta'ba tsammanin ma zai neme ni ba ganin irin jimawar da muka yi jiya muna abu daya. Abu na biyu kuma a tunanina gagarimin rashin da ya yi zai dakusar dashi kewar komai na jin dad'in duniya ashe ba haka abin yake ba fahimtata ma kamar idan yana cikin damuwa ya fi kulafucin lamarin washe gari na tashi da ciwon jiki matsananci domin irin sarrafuwar da na yi a hannunsa a daran jiya Ina ganin ko ko kwa'babbiyar fulawar borodi ba ta kaini buguwa ba.
Ina kwance gado bayan na yi wanka na kasa tafiya gidan rasuwar Yusi ya shigo yana gaya mini wai anti Nabila kanwar Hajiya Maryam tana kira na zo

ko zan iya rarrashin antin nasu ta karya kumallo. Na ce masa ya je ganin zuwa yanzu. Da kyar na rarrafa na tashi na sanya hijabi  saukata kasa ta yi daidai da shigowarsa hannunsa da ri'ke da carbi da alama daga wurin kar'bar ta'aziyya ya taso ya ce mini na je maza wurin Hajiya Maryam na zauna tare da ita yanzu Adam yake sanar dashi an yi an yi da ita ta ci abinci taki ci.
Na ce yanzu Yusi ya zo ya sanar da ni. Na fahimci tunda aka yi rasuwar yake bawa abinda ya danganci matar muhimmanci don jiya ma shine ya k'arfafa mini gwiwar zama a kusa da ita a cewarsa zan deba mata kewa bayan 'yan uwanta. Ban ta'ba kawo komai ba a cikin raina abinda dai na ajiye shine bai ajiye lamarin  Alhaji Amadu a nesa ba domin kuwa Allah ne kadai yasan irin taimakekeniyar da suka yi wa juna ba a lokacin da suke neman rufin asiri na duniya.
Hajja suka sauka kamar yadda ya fad'a Hajiya Saratu da kannan mahafinsa su biyu Maza a ciki akwai mahafin matashi ta biyu wato Aysha wadda ta rasu sakamakon zazzabin typhoid kafin ta tare a gidanshi.
Ba sosai na sansu ba duk da kasancewar suna da yawa kad'an na sani daga cikinsu, hakan yana da ala'ka da rashin zamanmu a gari tun bayan aure dangin Hajja ma in banda rasuwar da aka yi ta kanin mahaifin Hauwa babu wanda nasani daga cikinsu.
Wannan karon mun sake sosai da Hajja da alama sihirin da aka yi mata ya warware babu wani kallo na baibai a tsakanina da ita sai mutunci da girmama juna.
Haka aka yi zaman makoki na kwanaki bakwai mutumin nan bai  daga kafa ba. Kullum da safe zai fita cikin jama'a ya kar'bi gaisuwa da daddare kuma sai ya rikid'e ya koma jarababbe na bugawa a jarida.
Wannan dalilin ya sanya na yanke shawarar guduwa ba zan iya ba don ban san abinda ya zama ba kuma idan zai jima anan din bai koma legos din ba Hauwa sai ta zo ta kar'bi lamarinsa domin dai sha'aninsa ya fara ba ni tsoro da mamaki.
Ban sanar dashi maganar data assasa mini zuwa ba sai bayan an share makoki kwanaki tara da rasuwar tukkuna na gaya masa amma ta sigar da ba zai zarge ni ba ai taimako ne kuma duk wanda ya taimaki wani Allah zai taimake shi sosai na gaya masa yadda alhaji Muntari ya dinga fad'i tashin akan lamarin yarana kuma ya rike mini su ba tare da ya bambamtasu da wanda ya haifa ba, na kara jadadda masa cewa abinda ya asassa mutuwar aurena dashi akansa ne saboda rubutun da na yi a fece book akan abinda ya faru wanda ya danganci Kamalu dashi.
Bayanin da na yi masa cikin nutsuwa ya sanya ya fahimce ni ya kuma tausaya mutuka da gaske koda yake dama shi mai tausayi  dalilin da ya sanya mini fargabar gaya masa saboda tsohon mijina ne ban san fassarar da zai yi mini ba. A take a lokacin ya ce na yi waya da Baba Sule duk abinda muka tattauna sai na sanar dashi zai taimaka in sha Allahu.
Ban yi kasa a gwiwa ba kuwa na kira Baba Sule a waya ya gaya mini har yanzu dai ba kai ga kar'bar kudin gidan ba domin duk wanda zai zo tayin wulakanci yake yi. Na ce masa to abar batun sayar da gidan za a biya masu hakki hakkinsu insha Allah rabbi duk wanda yasan yana bin Alhaji Muntari

kudi ya yi mini list din sunansu  a takarda tare da asusun ajiyarsu idan na dawo sai ya kawo mini ni kuma zan tura masa sunayensu ta whasap sai a biya su hakkinsu.
Na sanar dashi yadda muka yi da ya ce hakan ya yi amma fa na ajiye maganar tafiya don su Hajja ne kadai za su tafi bi ba yanzu sai nan da kwana talatin lokacin Alhaji Amadu ya yi arba'in da rasuwa shi ma kuma a daidai lokacin zai koma bakin aiki can Legos.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*58*
Zaune na tashi ina goge hawayen idonta na dube shi sosai kafin na ce." Ba ni da ajandar komawa gidan Alhaji Muntari domin kuwa da da niyyar hakan a cikin raina wallahi tallahi da kaddarar aure ba ta ratsa tsakanina da kai ba."
Na numfasa Ina kallonsa yayin da shi kuma ya sake hade fuska tare da zubo mini ido da yanayi na neman rikici a tare da shi.
"Abu daya zuwa biyu ya sanya ni kokawa da rasuwar bawan Allan nan ko ka yarda ko kada ka yarda bai dame ni ba na farko shine hallacin da ya yi mini a lokacin da nake buk'atar agaji ya yi mini da kudi da karfinsa daidai gwargwado. Na biyu yadda gidansa ya tarwatse tun yana raye yaranshi suke walagigi ina ga kuma bayan rasu. Maganar nan da muke yi da kai a yanzu hankalina nakan babban yaronshi Turmuzi wanda tun asali nasan da cewa fitinanne ne an ce mini yanzu lamarinsa ya sake ta'barbarewa, ba zan manta ba mahaifinsa ba ya sha kokawa akan sha'aninsa. Wad'annan abubuwa biyu dana lissafa maka sune suka fi tsaye mini a rai  domin kuwa na riga nasan sha'anin zumunci a yanzu ya zama abinda ya zama tunda can ma danginsu ba masu zumunci ba ne balle yanzu da baya raye kuma dama shi kadai ne mai dan rufin asiri a cikinsu. Ni uwa ce kuma na yi gwagwarmayar rayuwa da yarana nasan zafin da ake ji idan aka rasa wani 'bangare dalilin da ya sanya kenan nake tausayawa Anti Maimuna uwargidanshi domin ita amaryar ta gudu ta watsar da yaran yanzu gabad'aya suna hannunta kusan su tara ka gaya mini ya za ta yi dasu wane hali za ta shiga domin ciyar dasu da basu tarbiya.
Shiru ya yi bayan na kammala maganata ya gyada kansa a d'an kausashe ya furta." Wannan shagube ne kawai Amina, ni kike so ki yi wa guri a matsayinki na uwa ko?"
Na yi kasa'ke ina kallonsa tare da auna maganarsa domin na gaza fahimtar inda ya dosa.

Ya d'ora da cewa." Af ai ni na uba ba ne, tunda ban haihu ba ban san zafinta ke da ki ka haihu ke ce ki ka san ciwon haihuwa."
Jikina ya d'an yi sanyi jin yana nema ya canza magana nasan hakan baya rasa nasaba da masifar kishin da yake kasa sarrafa shi shine dalilin da ya sanya yake jujjuya maganar dole sai ya fusata ni.
Sai kawai na share shi ban sake cewa masa komai ba na koma na kwanta hawayen na sake bin gefan fuskata. Ni har ga Allah mutuwar Alhaji Muntari ta dake ni sosai na kuma kara tabbatar da cewa duniyar nan aikin banza ce. Wannan ya sanya ni rushewa da kuka da karfin gaske ina Kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ya kuwa zabura! da ganin yadda nake kuka haikan!  Sai jikinsa ya yi tubis ya matso kusa da ni sosai yana d'an jijjiga kafafuna da hannunsa. Na sake tsananta kukan da nake yi had'e da jan hanci.
 Ya nisa sosai kafin ya  furta Yi shiru, yanzu dai Allah Ya jikansa abinda zan ce kenan, sai abu na gaba ina so ki gaya mini yadda kike so ayi tunda ai ni  na zama rumfa sha shirgi muddin wannan hawayen zai tsaya ki fad'i yadda ki ke so a yi miki zan yi in sha Allahu."
A hankali na dube shi ina nazartarsa akwai sasaauci a fuskarsa da kuma alamun tausayi da nadama kuma tunda ya ce zai yi to babu shakka kuwa zai yi din."

Na tashi zaune. Ya sanya tafin hannunsa na dama yana taya ni goge fuskata. Na ja hanci a karon da ba zai lissafi ba. Na ce." Ni abinda  nake so kawai wannan yaron nasa Turmizi a d'auke  shi a kai makarantarsu Kamalu bayan haka kuma ka shirya mana zuwa gaisuwa ni kuma zan zauna da anti Maimuna mu tattauna idan ya kama sai a bata jarin da zata kama sana'a ko?"
Idonsa a kaina ya ce." Hakan ya yi miki?" Kaina na daga. Sai ya ce." Ai ni mai aiwatarsa ne tunda haka ki ka tsara shikkenan za mu je amma sai bayan an yi addu'ar arba'in din Alhaji Amadu idan na yi musu ta'aziyya daga nan sai na wuce Legos abinda na manta ban gaya miki ba kuwa hajiya Maryam  ta bukaci akan na bar mata Yusi dalilin sha'kuwar da take tsakaninsa da yaranta akaran kaina ban so hakan ba sai dai ba yadda zan yi ne a yanzu tana buk'atar rarrashi da kuma biye mata akan dukkanin abinda take so domin dakushe mata kewar maigidanta, na san macace mai kokari sosai za ta kula da yaron kamar nata sannan ta yi alkawarin mayar dashi makarantar da Adam yake zuwa sai ya cigaba da dora karatunsa ina fatan babu matsala ta b'angaranki ko?"
 Haka kawai na ji ban ji dadin saurin yanke hukuncin da ya yi ba. To amma ba yadda zan yi koda kuwa raina bai so ba haka zan kar'bi hukuncin da ya yanke na tabbatar da matar tana da wata matsala mai muni ba zai bar mata yaron ba.
Washe garin ranar da aka yi addu'ar cikar kwanakin arba'in na rasuwar abokinsa kamar dai yadda ya fad'a muka nufi kano bayan ya jima a gidan abokin nashi wanda na tabbatar da cewa ya shiga ne domin yi masu sallama

da kuma kara tausarta yadda yake nuna kulawa da iyalin marigayin nake ji kamar kafin rasuwar tasa ya bar masa wasiyayyar hakan ne
Gidan Hajja muka sauke ta ce itama sai a yi tafiyar da ita don haka muna idar da sallar la'asar muka nufi gidan Alhaji Muntarin dake kawo jirga inda na zauna yau kwanaki hud'u kenan da rasuwar an tashi daga zaman makokin sai kad'an daga cikin 'yan uwanshi sai kuma Babanmu tare da Baba Sule da suke zaman jiran isowar isowarmu tunda mun yi waya dama.
Kai tsaye cikin gidan muka nufa ni da Hajja Yallabai din ya tsaya daga waje tare da Babanmu da jama'ar da suka ankara dashi.
Kasa juriya na yi ganin yadda anti Maimuna ta zabge ta zama kamar mashiriciya ba komai ne ya janyo hakan ba kuwa sai jinyya da fargaba da zullumi na rayuwa. Tana tare da kakarta wadda itace ke zaune tare da ita don ta d'eba mata kewar takaba sai kuma yaran gasunan sun kara girma Salimat ta zama cikakkiyar budurwa sai dai dukaninsu babu wata sutturar arziki. Sun gane ni gabad'ayansu suka dinga gaisheni na yi musu ta'aziyya na tambayi anti Maimuna Turmuzi ta ce mini tun washe garin ranar rasuwar uban ba su kara ganinshi ba.
Nan ta shiga warware mini halin da suke ciki da yadda wasu daga cikin ma'kotan da akayi zaman arziki suke dan taimaka musu ta ce mini ai tun kafin rashin lafiyar maigidan nasu ta yi tsanani Jamila ta gudu ta ce ba zata iya ba kuma duka yaranta ta bari ko bata fadi mini ba na gansu da idona. Muka ci kukanmu muka ko shi ni da ita don kasa ha'kuri na yi a lokacin da take ba ni labarin tana kuka ina yi ina kallon Hajja ma tana share hawaye domin kuwa kowanene dole ya tausaya rayuwar kuncin da suke ciki. Shigowarsu ita ta sanya muka yi shiru Yallabai din tare da Babanmu Baba Sule da 'yan uwan Alhaji Muntarin suka yi musu jagora.
Sosai ya yi wa anti Maimuna ta'aziyya ya kuma jajanta mata kwarai tare da yi mata nasiha mai ratsa zuciya da kawo misalai mababambamta daga karshe kuma ya kare maganarsa da jadadda mata cewa zai taimaka mata iyakacin bakin kokarinsa.
Godiya kakarta ta dinga yi har da kuka Hajja ta dinga bata baki akan ta daina kuka hakan ba komai ba ne face taimakon kai da kai idan har bai yi hakan da dukiyar da Allah Ya hore masa ba sai ta zame masa masifa.
Mun tattauna sosai da anti Maimuna inda muka tsaya a matsaya guda daya cewa bayan ta fita daga takaba zata fara gudanar da kasuwancinta a cikin gida za ta duba abinda ya fi saurin tafiya a unguwar sai ta kafa kowa rabonsa zai samu.
Muka nufi gidan Hajiya Dogara domin yi wa mahaifiyarsa ta'aziyya. Matar da kyar take iya kallona saboda nauyi da kunyar abinda ta yi mini akan Kamalu ta dinga godiya kamar ta yi kuka domin alherin da Yallabai din ya yi musu na saukewa mamacin tarin bashin da ake binsa tun kafin ya yi bankwana da duniyar.
A ranar da daddare ya aiki Sukairaju da kayan abinci da masarufi masu yawa gidan Alhaji Muntari.
A gidana muka sauka gabad'aya har Hajja domin ya fi kusa da Dambatta ga dare ya yi Hajja ta ce da safe ta tafi ba ta son tafiyar dare.

Baba Tabawa da Yusura sunan lafiyar Allah kamar ina tare dasu domin abinci da kayan masarufin dake store dina ina tsammanin za su iya hauraa shekara basu kare ba. Bayan haka kuma akwai masu tsaro a gidan kuma mun yi waya da Sahura sati daya da tafiyata na ce ta dinga zuwa gidan tana duba su duk sa'i da lokaci.
Baba Tabawa kuwa aka ci sa'a ta yi favorite dinsa towon dawa amma miyar ku'bewa bushashshiya sai dai ta wadatu da daddawa da nama sai k'amshi take yi. Aikuwa ya ci sosai har yana tsokanarta wai ta fi ni iya abinci dama idan na yi towo ha'kuri kawai yake yi yana ci. Hajja itama ta yaba mata sosai ta ce mini a ajiye mata d'umame da safe kafin ta tafi sai a d'umama mata shi. Baba Tabawa tace ai kamar ta sani ta yi shi da yawa.

Kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biyani hakkina ba

Had'uwarmu ta daran yau sai ta zama ta daban domin kuwa lamarin da ya bijiro dashi bai samu kar'buwa ba a wajena yayin da shi kuma ya kafe kai da fata sai ka ce wanda aka yi wa wahayi lallai ta haka yake so ya biya bukatarsa to sai bijirewata ta wanzar mana musayar yawu domin kuwa ni dai ban ta'ba jin inda aka yi wata kwanciyar aure a tsaye ba. A ganina ma ta wannan sigar ta yaya mutum zai fahimci wani abu ya za a yi lamarin ya yi armashin da kowa zai gamsu. Ya dage shi fa ga ta yadda zai yi domin sai ya fi gamsuwa a cewarsa ko ya koma zai jima sha'awarsa ba ta motsa ba ni kuma na ce ba zan iya jurar tsayuwa ba na amince a yi akwance duk yadda yake so zan yi amma a tsaye ba zan fahimta ba. Ai lamarin na mutum biyu ne ba na mutum d'aya ba. Sai ya fara fad'in ai Ubangiji ya ce ku shiga gonakinku ta kowace siga amma ban da ta waje daya don haka shi yau zai gwada yi a tsaye. Tun abun yana ba ni dariya da mamaki har ya dawo ba ni haushi da ganin kamar yana so ya sauka daga koyarwa addinin musulunci ya bi turbar nasara domin kuwa sune shaidanu masu kirkiro abun da zai cutar da mutane.
Ya ce idan ba zan amince ya yi ta haka ba kuwa sai da na yi sucking dinshi har ya biya bukatarsa. To dama dama wannan da sauki tunda wani sa'in ina yi masa amma ba sosai ba don baya ganewa muddin ba wajan nan ya shiga ba. Ya za a yi sucking ya iya gamsar dashi a yadda yake sai mu kwana ba mu rintsa ba. Amma dai na fi aminta da yin hakan akan ya yi a tsaye k'afafuna ma ba zasu iya jurewa ba.
Sarewa na yi da sha'aninsa domin kuwa duk tsayin lokacin da na d'auka ina yi masa abinda ya buk'ata din ko gezau bai yi ba wai da sunan samun satisfying yana dai nishad'antuwa k'warai da gaske tabbacin yadda nake yi masa yana jin armashi ammafa babu wani shau'ki na kawowa.
Gajiya na yi kawai na matsa gefe daya domin kuwa kafad'una sun k'age dalilin sunkuyo jikina ma gabad'aya ya yi tubis bacci ne yake mamayata. Ganin haka ya sanya ya janyo ni a ki'dime ya fara sarrafa ni akwancen dai ya biya bukatarsa amma ta siga daban daban. Ni kam duk wanda ya bashi shawarar yin amfani da maganin k'arfin maza ya cutar dashi domin kuwa

abin nasa yana nema ya yi yawa. Da sassafe ya shirya yana ta zoyalata zai tafi amma zai dinga zuwa ta mafarki. Na.dinga zumbura baki ina fad'in duk wanda ya baka shawarar yin amfani da maganin karfin maza ya d'ora ka a hanya mara b'ullewa ai ba a ce kada a yi jima'i ba amma daidai misali yanzu baba don Allah wane hali zaka shiga a can babu mace a kusa......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*59*
To sai a lokacin ya ke gaya mini shi babu wani maganin karfin maza da yasha hana karya dai ya yi amfani da maganin sanyi watanni uku da suka wuce lokacin da Falalu mai yi masa abinci ya je garinsu mahafiyarshi ta bashi ya kawo masa a matsayin tsaraba. Falalun ne ma da kanshi ya dafa masa maganin da yake sassa'ke ne da saiwowi ya had'a da citta kaninfari tafarnuwa ya dafa shi sosai ya zuba masa a babbar gora ya yi amfani dashi.....08089965176 Wallahi maganin sanyi ne sadidan har basir ma yana lalata tasirinsa a jikin dan adam. Kaikayin gaba zafin fitsari fitar iska rashin ni'ima zubar fitsari karancin sha'awa ciwon mara ciwon kafafu rashin haihuwa. Ciwon ga'bo'bi rashin gamsuwa maganin kuma maza da mata ne duk wani dattin da yake mara za a fitsarar dashi, ga masu buk'ata a yi mana magana kai tsaye ta lambarmu da muka d'ora za a yi wa Allah godiya kuma za a yi mana godiya.

Na yi mamaki sosai da na ji ya fadi haka. Dama ai duk lalacewar namiji wajan saurin kawowa ko rashin dogon zango ko kuma daukewar sha'awar da kankancewar gaba gabad'aya sai dai idan bai yi katari da sahihin magani ba. Haka zalika ma duk lalacewar mace wurin rashin ni'ima bushewa da fitar iska, d'aukewar sha'awa da matsalar rashin gamsuwa daga maigidanta sai dai idan ba a yi katari da ingantaccen magani ba. Haka zalika ma 'yan mata da zawarawan da suke da niyyar shiga d'akin mazajensu yana da kyau su ma su magance sanyin da yake tattare dasu domin gujewa matsala...08089965176 a tuntub'e mu kai tsaye muna tura kayanmu kowane gari.

Bayan kwanaki uku da tafiyarsa yanayin jikina ya fara canzawa lamarin ba sabon abu ba ne a wajena amma ban tabbatar ba dai tukkuna har sai da lokacin yin la'adata ya yi ya wuce ban yi ba yayin da ciwo-ciwon da nake ji yake 'kara tsananta. Kakarin amai da safe taruwar yawu kasala saurin bacci da k'yankyami. Ciki ne da ni ba shakka lamarin bai yi mini wani armashi ba

domin kuwa ban shirya d'aukarsa ba kuma ba na tsammanin zan gaya masa har sai na yanke shawarar da nake ganin itace mafita ga rayuwata.
Ko anti Yagana ba zan gayawa ba balle ta dakusar da ni domin kuwa yana da kyau komai mutum zai yi ya kiyaye faruwar abinda zai sanya shi shiga rud'ani a gaba.
A takarda na rubutawa Yusura abin gwaji ta fita bakin titi akwai chamis ta je ta sayo mini da sassafe na yi sakamako mai kyau ya fito positive. Shiru na yi da bakina kuma na dinga kokarin ganin na karfafi jikina don kada Baba Tabawa ta fahimci halin da nake ciki. Ba Allah zan yi wa butulci ba amma ya fi ni sanin dalilina na yin hakan zan nemi maganin da cikin zai fita tun kafin ya kai matakin da za a busa masa rai a yanzu dai bai wuce kwanaki a arba'in ba na tabbatar da samuwarsa ne had'uwarmu ta farko dashi zuwana Abuja tunda lokacin da na je ban fi sati daya da yin wankan tsarki ba kuma ni ba ban yi amfani da wata kariya domin gujewa faruwar hakan ba. Mun had'u sosai tun kafin ma na tafi maiduguri mun yi kwanciyar aure amma rabon bai rantse ba sai yanzu.
Da kaina na fita da daddare bayan Isha'i cikin hijab har kasa da nikabi har da safar kafa domin yin b'adda kama na nemi maganina na dawo gida.
Zuciyata tana dokawa a daran ina ta shawarwari nasha ko kada nasha domin sai nake ganin kamar Allah zai tuhume ni kuma ba zai kar'bi uzurina ba tunda tun farko ai ba a san da menene silar dake haifar da ciwon ba iyaye da kakanni haka suka yi auransu ba tare da sanin matsayin jini ba. Domin kuwa da yawa As da As  suna yin aure ba su  san alakar jininsu ba kuma su yi haihuwa fiye da goma ba tare da samun wani mai lalura ba. Da yawa kuma akwai masu S A da S A din da suke aurensu lami lafiya su gama haife haifensu ba su ci karo da komai ba kuma yaransu duk yawansu suna rayuwa. Kamar yadda anti Yagana tasha gaya mini turawa ne suka kawo wannan rikitarwar har aka kafa doka mai k'arfi akanta. Akwai ciwon ba wai babu ba to amma babu hujja mai karfi wadda za a  guji auratayya domin raya sunnar Annabi Muhammadu S.A.W.
Cike da cajin kai da zullumi tare da fargaba na sha maganin amma daya nasha sabida yana da k'arfi dayan kuma na yi flushing dinsa.
Wajan karfe uku na tashi da matsanancin ciwon mara da baya, tare da cijewar kafafu. na dinga murkususu ni kadai don sallar asubahi ma sai da safe na yi ta. Abin karin kummalo d'akin Yusura ta kawo mini domin ban Kai ga fita falon ba ina kwance a gado murfin gwiwata sai ciwo yake yi mini da kafafuna kasan marata amma babu d'igon jini a pant dina sai da uban ciwon dai.
Na dinga zurga zurgar zuwa bandaki ina dubawa babu wata alamar zubar wani abu. Jikina ya mutu murus na yi kwance a gado ina istigifari ga Allah lallai duk yadda na kai ga so cikin ya fita idan fa Allah bai kaddara ba sai dai na ci wahalar kuma na haife shi babu yadda zan yi
Idan kuwa aka yi rashin sa'a na shiga hadari gagarimi  sakamakon shan maganin  da na yi cikin bai fita ba kuma ba ni da tabbacin cewa yana cikin 'koshin lafiya sakamakon yun'kurin zubar dashi da aka yi da ganganci.

Hawaye ya shiga silalowa daga idona tausayin kaina ya kama ni. Na ha'kura kawai na barwa Allah lamarinsa muddin cikin nan bai fita ba kafin yamma to ba zan yi yun'kurin sake zubar dashi ba. Duk abinda Allah Ya yi daidai ne.
Da k'yar na iya kur'bar shayi na ci dankali da 'kwai kad'an na sake kwanciya da wayata a hannuna zuciyata na tashi yayin da nake dan jin sasaauci daga kasan marata na rintse idona a hankali ina tasbihi ga Allah tare da sake jaddada istgifari domin neman afuwata.
Bayan azahar sai ga Sahura da ma mun yi waya da ita ta ce mini za ta zo a cikin satin da muka shiga. Dole ta sanya ni k'arfafa jikina domin kada ta fahimci wani abu amma duk ko'karin da na yi gurin kwarara gwiwata sai da ta gane ba na jin dadi ta fara zolayata wai ko nayi tsaraba daga abuja ne domin wallahi alamun mai yaron ciki ya bayyana a tattare da ni. Bagarar da maganarta na dinga yi na ki ba bata muhimmanci har ta yi ta gama ta fara gaya mini an zo tambayar auran Yusura kuma za a kawo kudin auran ranar juma'a wannan din nan ne dai dan gidan Yayar babanta wanda na tambayeta ta ce mini shi take so kwanakin baya sosai na yi farinciki da jin haka domin duk wani bincike sun yi tana kuma jadadda mini cewa yaron mane mi ne mai zuciyar neman na kansa kuma yana can yana gini a sabuwar unguwar nan ta rimin auzinawa. Yadda ta dinga zolayata ni ma haka na dinga zolayata ina dariya ta tsufa don ana yi wa Yusura aure shekara daya za ta haihu dole ta dau'ki jika. Fad'i take ai tare muka tsufa domin kuwa 'yar ki ce ba tawa ba.
Sai da ta yi sallar magriba tukkuna ta yi shirin tafiya na sanya sabon direban da aka ajiye mini ya dauketa a mota ya kai ta har gida.

To mukan d'an yi waya da maigidan sa'i da lokaci amma mafi akasari shi yake kirana idan ya samu sukuni ba sosai ya fiye amsa waya ba sai mai mutukar muhimmancin gaske Amma fa shi yana kirana a duk lokacin da yake da isheshhen lokaci sai mu fi karfin awa daya muna hira ta waya sosai. Amma fa ko da wasa ban ta'ba kuskuran gaya masa wani abu ba tunda cikin bai fita ba na bar shi kawai duk lokacin da ya zo garin sai ya gani da idonsa.

Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta shi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Bayan wata biyu da dawowo ta ina lissafin watannin cikin dake jikina wata uku da kwanaki kenan wannan karon laulayi nake yi sosai domin kuwa ba komai nake iya ci ba na fi kauri dai a b'angaran manja da yaji wainar fulawa ko d'anwake da manja ko d'anmalele. Sai ko kayan gona wannan kuma Hamusu nake sanyawa ya sayo mini duk bayan kwana uku ya kawo mini hidimar soya waina da danmalele kuwa Yusura ce ke yi mini. Duk cika da kasaitata a ko'ina sai da na rairaye saboda azabar laulayi ban fita na je ko'ina ba balle a gane halin da nake ciki itama Sahura tun zuwan da ta yi bata sake zuwa ba sai dai mu yi waya. Anti Yagana ma waya muke yi kuma ban gaya mata komai ba. Ta ce mini dai karshen shekaran nan za ta zo amma ita

kad'ai ba tare da yaran ba saboda makaranta. Muka tsaya akan zuwanta a karshen shekaran nan da muke ciki to sai dai kana taka Allah Ya na tasa domin kuwa rikicin da ya ritsa da Hadiza shine abinda ya tilasta mata zuwa ba tare da shiri ba.
Hadiza garin neman duniya da son lallai sai ta yi kudi bayan tafiye-tafiyen da take yi zuwa dubai sarin kaya ashe ta had'a kai da wata mata da suka hadu a can dubai din itama 'yar kasuwa ce mazauniyar Na'ibawa anan gidanta yake kuma bazawara ce babba da yaranta ta ribaci Hadiza tare da kwaid'ata mata kudin da zata samu idan ta shiga 'kungiyarsu ta shan jini. Ba tare da dogon nazari da tunani ba tunda dama babu wani sanin addini a tare da ita ta fantasma kanta a harkar da babu fita muddin an shigeta kuma sharad'in shine dole sai mutum ya bada jinin dan adam mutum guda.
Suka had'a baki da ita Hajiya Alili suka saci wani almajiri suka mika shi ga kungiyar kamar yadda suka buk'ata da da farko cewa suka yi da ita sai ta bada d'anta na cikinta ta ce musu ai bata taba haihuwa ba shine suka buk'ace ta cikin kwanaki biyu kacal ta kawo musu matashin yaro wanda bai balaga ba.
Matsanancin tashin hankali muka shiga gabad'ayanmu domin lamarin da ya faru sai yake nema ya shafi zuri'armu gabad'aya mutane suna ta ririta maganar tare da 'kir'kiro k'arya da gaskiya har da masu cewa dama sun jima suna zargin alhalinmu ko maita ko karuwanci ashe 'yan mafiya ne, wasu kuma na cewa gidan namu dama ai ya yi 'kaurin suna yara tun suna k'ananu suke sace sace......✍

Mun shiga book3 anan har mun yi rabi fa, ina ga ya kamata ku shi mini albarka don ban ta'ba kawo muku wani uzuri ba kullum sau biyu kuke samun update sannu sannu bata hana zuwa😃 Na gode muku sosai.
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*60*
Hadiza ta zama kamar zautacciya domin kuwa ita da mahaukaciya marabarsu kalilan ne zafin addu'a da irin saukar karatun al'kur'ani da ake yi akan 'batan yaron ya sanya da bakinta ta fad'i ta yi kisan kai domin kuwa yaron tuntuni an shanye jininsa hakkin rai da rashin sabo ya sanya nutsuwa ta yi kaura daga jikinta.
Yadda bincike ya nuna ita Hajiya Alili tunda ta ji maganar ta fasu a gari ta yi 'batan dabo aka nemata a ka rasa a garin. 'Yan unguwa suka cinnawa

gidanta wuta ita kuma Hadiza muna ji muna gani mota guda da 'yansanda suka tafi da ita. Tashin hankalin da ya assasawa Babanmu fad'uwa kenan ranga ranga rai a hannun Allah muka kai shi asibitin nuna koke-koke don wallahi ni tsananin damuwa da fargaba ya sanya na manta halin da nake ciki duk wasu lalure laluran da nake yi a tsaitsaye nemansu na yi na rasa saboda tsananin tashin hankali da fargaba don sai na ce na jima ban ga abinda ya daga mini hankali kamar wannan lamari ba. Da yake tunda ta bar gidana ban sake ganinta ba sai da wannan abin ya faru gabad'aya kammaninta sun canza ta zama kamar wata tsohuwar kilaki hujin hanci biyu kowanne da barima a sak'ale har da sarkar kafa a kafarta ta hagu. Hankalina ya sake tashi a fakaice na dinga share hawayen tausayi da nadamar duniya domin dai Hadiza ta gama tona mana asiri ta 'bata mana nasabar gidanmu, ta ci mutuncin Babanmu yanzu da muna da sauran 'yan uwa mata da wahala su auru da wuri dalilin wannan abin kunyar da ta janyo mana. Anti Yagana tana da juriya sosai ban ga kwalla a idonta ba amma a gigice take mussaman da Babanmu ya fadi. Ita kam Fati dama tana da iskokai domin tun tana yarinya sun taba nunawa zaman bori tayi a tsakiyar tsakargida suka dinga haurowa kanta suna ifece-iface anti sakina ita ce taje ta gurfana a gabanta tana yi mata addu'a.
Muka dinga zurga da kai kawo daga gidanmu zuwa asibiti zuwa ofishin 'yansanda. Ni da anti Yagana mune manya kuma mune masu rufin asiri a ciki. Itama Ummansu Hadiza sun ri'ke dukiya a da can domin mahafinsu tsohon mai kudi to amma yanzu babu domin duk rabinsu sun karye dalilin fafar da suka dinga yi da kudin gadon, kuma dama kaf gidansu babu wani fitacce wanda ya samu ilimin addini sun taso da jin dadi da gata irin na mahaifi wanda shi din aka shede shi mutumin kirki ne, kuma dukiyar da ya tara musu ta halak ce domin ko da can ma baya had'a hanya da riba. To babu
abin yanzu da yawa wasu daga cikin danginta ma sukan rasa abinda za su sarrafa a cikinsu su bawa iyalinau. Ga masifar da take ciki bata fita ba wata ta kara kutsowa Alajiji d'anta na fari da ta haifa a wani gidan ya je ya damfari wani makudan kudi asirinsa ya tuno yana hannun hukuma suna bincike akansa domin dama tsohon mai lefi ne ya jima yana harkar yahoo 419 shine kiran da ta yi Alhaji Tajo a kwanakin baya ta ke gaya masa ya taimaka musu. Son zuciya ɓacinta kuma duk wanda ya sayi rariya tabbas ya san sai ta zubda ruwa idan da godiyar Allah iya jarin da Alhaji Tajo ya bata ya isheta ta juya ta kuma ri'ke kanta har ta kula da wasu to amma ta sanya son zuciya da son dole sai ta yi kudi ta kowace hanya ga abinda ya janyo mata nan.
Anti Yagana a gidana ta sauka wannan dalilin ya sanya muke zurga zurgar tare domin ba zan ta'ba bari ta yi ita kadai ba. Hankalinmu bai kwanta ba har sai da muka ga jikin Babanmu ya dawo yadda yake tukkuna muka samu nutsuwar tattauna yadda za a kamo bakin zaran matsalar da Hadiza ta rikitowa kanta. Lamari ne gagarimi wanda duk wanda ya ji abinda ta aikata ya jajanta mata don gaskiya da wahala idan hukuncin kisa bai rataya a wuyanta ba gashi an yi an yi da ita ta fad'i wurin da mutanan da suka sanyata suke ta'ki fad'a duk kuwa da azabar wahalar da take sha a hannun

hukuma. Ranar da muka je da dubata alfarma kawai suka yi mana dalilin ina auran Babban mutum amma da babu wani uzuri da zai sanya su bar mu shiga wajenta. Kuka wiwi na dinga yi ganinta a jigace ta dimauce jikinta duk shacin duka abinka da farar fatar da aka had'a mata da man bilitin ta ki'dime sosai tana ta zantuka marasa tushe anti Yagana ce mai dauriya bata koka ba amma idonta kadai ya  tabbatar mini da cewa kukan zucci take yi. Fati kam fad'uwa ta yi a wurin aljanu suka bugeta a karon da ba zai lissafu ba domin tunda aka kama Hadiza take iskokai
 Hassana da Usaina suka fita da ita can waje domin wurin da muke babu iska. Da muka fito anti Yagana ta gargadi su Hassana akan kada wadda ta kuskura ta gayawa Ummansu halin da muka tsinci Hadiza su nemi hanyar da zasu kwantar mata da hankali koda kuwa ta 'karya ce don za ta iya shiga mummunan yanayi muddin ta ji halin da Hadizan take ciki.
A daran aka sallami Babanmu daga asibiti a waya na kira Ayuba sabon direba na ce dashi ya zo ya d'auke mu a mota gabad'aya domin a galabaice nake kwarai da gaske gajiya da jiri da ciwon mara da kafafu ban kuma kawo komai a raina face wahala da fargaba tare da kai da kawon da na yi.
Muna komawa gida ni da anti Yagana na zube a tsakiyar d'akina domin wani mashahurin ciwon mara ne ya turnike na dinga murkususu ina ri'ke cikina anti Yagana hankalinta ya tashi sosai ta kira Baba Tabawa tana cewa mu je asibiti na girgiza mata cikin halin da nake ciki na fara yun'kurin amai amma bai fito ba kakari na ke yi ban amayar da komai ba sai can na ji kamar an fasa ruwan pure water a zanina jini mai yawa ya fara gudana har ya fara naso a kafet din daidai inda anti Yagana ta ajiye kafarta. Cikin fitar hayyaci na furta." Anti Yagana 'bari zan yi jini ne yake zuba."
A ki'dime ta tsuguna gabana ta daga cinyata jini sharkaf ya jika mini zani sai ta fashe da kuka tana fad'in." Ciki ne dake dama Amina Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ta k'walawa Yusura kira tare da ce mata ta gayawa Ayuba ya fito da mota za mu je asibiti. dishi dishi na fara gani domin kuwa kafin faruwar hakan na yi masifar tsorata da irin mahaukacin jinin da nake zubarwa wannan shine ya assasa d'aukewar ji da ganina na wucin gadi.

To cikin dai ya zube a lokacin da ban yi tsammanin fitarsa ba. Wahala kuma na ci ba 'yar karama ba domin kuwa biyu ne ashe na farkon ya fita ba mu jima da zuwa asibitin ba. Na biyu sai da aka kai ga yin wankin ciki tukkuna aka yo waje dashi. Jini kam na zubar ba kad'an ba aka dibi na anti Yagana aka sanya mini aka nemo leda daya  a waje a kara.
Tun a daran anti Yagana suka yi waya da maigidan ta sanar dashi halin da ake ciki. Ina jinshi lokacin da yake gaya mata ai ban ta'ba sanar dashi ina da juna biyu ba har wata uku da sati uku. Ya ce mata in sha Allahu gobe mu tsammaci zuwansa. Da safe Baba Tabawa da Yusura suka tafi gida domin yin abinci. Anti Yagana tana tare da ni a asibitin motsi kad'an sai ta dube ni ta share kwalla. Jikina ya yi sanyi na fara zargin ko likitan da yake tsaye a kaina ya yi mata bayanin wani abu ne. Ni babbar fargabata ma zuwansa asibitin nan domin kuwa gabad'aya na yi sanyi da lamarin dalili na riga na san

likitocin asibitin Malam Aminu suna da gogewa ta fannin aikinsu dole zasu yi binciken abinda ya asassa fitar cikin nawa.
Jiki babu wani kuzari na yi wanka da ruwan da ta had'a mini a bandakin dake cikin d'akin da nake kwance da yake waje na mussaman suka ajiye ni a asibitin dalili tun shigowarmu security suka shaida fuskata duk kuwa da yanayin da nake ciki na ciwo.

Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na shirya cikin doguwar riga na kintsa jikina sosai cikin rashin kuzari da k'warin gwiwa gabad'aya rashin walwala da sukuninta ya fi damuna sosai akan fitar cikin daga jikina.
Likitan da yake duba ni ya sake shigowa muka gaisa ya yi mini tambayoyi na ce masa jiri ne ya fi damuna sai rashin jin dadin jikina. Magunguña ya had'a mini tare da ba ni shawarwari da yadda zan yi amfani da maganin ya ce mini sun yi waya da Yallabai din ya ce ya iso garin amma yana dambatta wurin mamanshi zai jira zuwansa asibitin kafin ya tafi gida tunda dama aikin dare yake da shi.
Shiru na yi ban iya ce masa komai ba anti Yagana ta yi masa godiya kafin ya fita. Ina kallonta ta je ta yi wanka ta kimtsa jikinta ta sake zama a gefana ba ta da niyyar cin wani abu bayan gashinan Baba Tabawa ta yi abinci mai kyau Ayuba ya kawo. Na daure na yi mata magana a hankali ta dube ni amma ba ta ce mini komai ba. Na ce." Ba ki ci abinci ba anti Yagana."
Kanta ta girgiza a hankali ta furta." Ba na jin yunwa Amina har yanzu ban daidaita ba wallahi jiyan nan na shiga rud'ani ba kad'an ba sai nake ganin kamar za ki tafi ki barni ne."
Hawaye ya sake silalo mata.
Murmushi na yi cikin raina na ce dama abinda take yi wa kuka kenan. Anti Yagana kenan ai mutuwa kam ta zame mana dole ko na rigata ko ta riga ni babu wanda zai zauna a cikinmu.. Na daure na ce." Ni ma ban ta'ba jin ciwo mai azaba irin na jiya ba wallahi ni kadai nasan halin da nake shiga anti Yagana Allah dai ya takaita mini wahala."
Ta gyada kanta da kulawa ta furta." Gashi ma ashe 'yan biyu ne amma me yasa ba ki taba gaya mini kina da ciki ba Amina, ai ko baki sanar da kowa ba kya gayawa wanda ya yi miki jiya da muka yi waya yana ta fad'a shi bai sani ba."
A dan sanyaye na ce." Anti Yagana shurun da na yi masa shi ya fi alheri domin kuwa nasan halinsa idan ya samu labari zai hana kansa sukuni ne, ni a tawa fahimtar kawai na bari ne duk lokacin da ya zo garin sai ya gani da idonsa.
Ta ce." Wannan ba hujja ba ce ko dan gaba kada ki kara haka ai abin alherine kuma yana da hakki ki gaya masa. Baki san hakan zai yi masa ciwo ba kenan ga yanayin yadda yake magana a wayar ya tabbatar mini da cewa ya ji haushin abinda ki ka yi......✍

Akwai pege din da ban baku ba kafin wanda na jiya da daddare ban san yadda zan yi ba wurin tura muku shi. Wad'anda suke comments section zan tura can sai ku karanta mistake na yi wallahi ku yi hakuri.

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*61*
Na ce." Zan kiyaye in sha Allahu rabbi,
yanzu dai ki ci abinci ba na so na dinga ganin ki cikin damuwa da alhini duk abinda Allah Ya yi daidai ne fa anti Yagana don Allah ki daina daga hankalinki, dama can Allah Ya yi ba rayayyu ba ne."
Ta girgiza kanta da damuwar dai ta furta." Tabbas yadda Ubangiji ya yi shine daidai amma na so a ce kin haife tagwayen nan Amina, amma Ubangiji Allah Ya ba ki wasu, kin gaji Babanmu wurin haihuwar tagwaye ya yi sau biyu Hassana da Usaina da kuma na wurin Ummansu Saminu Hassanan da Usaini.. murmushi na yi tare da
Sunkuyar da kaina kasana furta." Dama ai an ce ana gadonsu bangaran uwa ko uba. Anti Yagana Allah dai ya ba mu masu albarka."
Ta amsa da Amin babu sukuni a tare da ita. Ni kuma na sake yin k'asa da kaina ina jin wani abu a can kasan raina
yanzu idan ba dan'uwanka na jini ba wanene zai gwada maka wannan soyayyar da tausayawa.
Tare muka ci abincin amma ni kadan na iya ci nasha maltina tana ci muna taba hirar lamarin Hadiza. Hamusu ya kira ni a waya ya ce gashi nan asibitin ya shigo dubani domin yanzu daga can gidana yake Yusura ta gaya masa ba ni da lafiya.
Anti Yagana da kanta ta fita ta yi masa jagora muka gaisa sosai dalili tunda na dawo daga abuja ba mu had'u ba sai a waya idan na kira shi ko ya kira ni dangane da harkokinmu ya ce zai tafi amma da yamma za su so tare da Gwaggo anti Yagana ta ce masa sai dai su je can gidana domin kuwa ta ji likitan yana fad'in ya rubuta takardar sallama yana jiran zuwan Yallabai din ne. Ya ce idan ba su zo da yamma ba to gobe da safe za su je can gidan muka yi sallama ya kama hanya ya tafi shago.
To sai bayan sallar azhar tukkuna suka zo asibitin tare da Hajja da Hajiya Saratu. Haka kawai sai na tsinci kaina da kasa had'a ido dasu gabad'aya domin hausawa suka ce mara gaskiya ko a ruwa gumi yake yi. Gabad'aya na kasa nutsuwa domin sai nake ganin kamar za a gane na yi wani yun'kuri a baya.

Hajja sai sannu take yi mini tana fad'in an auna arziki ai tunda cikin ya fita ba tare da wata matsalar ba. Hajiya Saratu ma ta jajanta mini sosai tana cewa idan da rabo a kusa sai a kara samun wani.
Shi kuwa ogan yana tsaye a gefan kaina tunda muka gaisa ya yi mini sannu bai sake magana ba yanayinsa dai ya nuna jimami da damuwar abinda ya faru. Jikina ya kara yin sanyi sai na  kasa daga kaina na dube shi a lokacin da likitan ya shigo d'akin yana tambaya ko da matsala na girgiza kaina alamun babu komai. Ogan ya dora hannunsa a saman goshina sai likitan ya dube shi yana cewa." Da zu da muka yi magana da ita ta ce mini jiri ne kadai yake damunta amma in sha Allahu shi ma zai gusa nan da kwanaki uku tunda an dubata sosai babu wata matsala sai ta rashin kwarin jiki, bayan haka kuma ga magunguñan nan masu kyau na hada mata."
Hannu ya ba shi suka yi musabaha da juna yana yi masa godiya yayin da likitan yake jadadda masa cewa babu godiya domin kuwa aikinsa. Tare suka fita sai hakan ya haifar mini da damuwa don sai nake ganin kamar akwai wani bayani da likitan zai yi masa wanda yake b'oyewa. Hira suke yi a d'akin tsakanin Hajja da Anti Yagana dama akwai shak'uwa a tsakaninsu tun zuwan da anti Yagana ta yi wajena a lokacin da ina Legos.  Ni kuma jikina duk ya yi la'asar hankalina na can tunanin abinda zai faru domin kuwa nasan ko likita bai gaya masa wata magana ba na tabbatar da cewa sai ya tuhume ni dalilin da ya sanya na yi shiru ban gaya masa samuwar cikin ba tsayin wattani uku da satika.
La'asar a gidana ta yi mana tare gabad'aya muka dunguma har dasu Hajja a ka yi sa'a kuwa Baba Tabawa tana ta hidimar abinci koda ta fito suka gaisa cikin barkwanci take cewa da maigidan towo take yi saboda ta ji labarin zai zo kuma ta sanya an samo mata daddawa da kuka masu kyau tunda ta fahimci ya fi k'aunar miyar kuka fiye da sauran abin ka'di.
Ya dinga godiya kuwa cikin kulawa da sakin fuska wannan dabi'ar tasa ta rashin 'kyama tana kara masa martaba. Hajja fadi take yi kin kyauta kuwa Tabawa sai ki tu'ka towon da yawa ni ma na tafi dashi na d'umama da safe.
Tashi ya yi ya nufi d'akinsa dake saman bene wanda ya jima a rufe tunda ni duk dabdalata a kasa nake yi ban sake hawa saman ba tun washe garin ranar da na tare a gidan.
Duk da rashin jin kwarin jikina hakan bai hana ni tashi na bi shi bayan shi ba. Waya yake yi da Sukairaju a lokacin da na shiga d'akin tare suke zo dama tunda shi ya d'auko mu a mota ma. Na nemi kusa dashi na zauna a hankali Ina nazarin d'akin bai yi wata 'kura ba tunda ko'ina rufe yake da tagogi irin na gilashi da narka narkan labuleye a kewaye babu ma wata kofa da k'ura za ta shigo  sai dai idan an dan gyara wasu guraran hakan ba zai zama lefi ba.
Ya kashe wayar yana dubana a tsanake ya furta." Ya gajiya da jikin kuma?"
A hankali na furta." Na ji sauki kai ma ya gajiyar hanya."
"Ban gaji ba." Yafada idonsa a tsaye a kaina. Sai na yi kasa da nawa idon ina dan jin fargaba kad'an zan yi kokarin ganin na kare kaina ta kowace siga domin kuwa na fahimci zallan rikici da fitina a cikin kwayoyin idonsa."
"Ina so ki gaya mini abinda ki ka taka, kada ki rufe ni Amina domin kuwa babu abinda na tsana a rayuwata sai zamba cikin aminci. Na kan ji na tsani

mutum tsana ta har abada muddin na fahimci cewa yana zaune da ni da wata zuciya ta daban. Ki fito fili ki gaya mini me kike nema a wajena? Menene a can kasan zuciyarki dangane da zama da ni."
Cikin nutsuwa na furta." Ban gane inda maganganunka suka dosa ba Baba."
Ya tsira mini ido da b'acin rai a tare dashi kafin ya gyad'a kansa ya ce." Kin san idan wani likita zai b'oyewa kowa wani lamari da ya shafe shi tsakaninsa da mara lafiyarsa ni dai alfarmata da yadda Ubangijina ya karramani a nan gidan duniya ba za a rufe mini wani lamari da ya dangance ni ba. Likitan da ya yi tsaye a kanki a daran jiya ya yi mini bayanin da ke kanki bai yi miki shi ba, ya sanar da ni dalilin zubewar cikinki wanda ki ka boye mini samuwarsa bincike ya nuna cewa lallai an yi yun'kurin fitar dashi ta kar'fi da ya ji, hakan ya haddasa matsala babba cikin ya canza mazauni, shi bai fice ba haka zalika kuma shi ba zauna daidai yadda ake so a mahaifar ba. Ya gaya mini biyu ne na farko ya fita jim kad'an bayan zuwanku asibitin na biyun ne sai da aka kai ruwa rana kafin su fitar dashi ko kina da ja akan hakan, ni dai na san Dr Iliyas haka kawai ba zai 'kir'kiri 'karya domin ya 'bata ki a wajena ya gaya mini ba, ya sanar mini ne domin akan akinsa yake ni kuma na aminta da bayaninsa sanin da na yi miki za ki yi aikata fiye da abinda ya fi haka. Na ro'ke shi ya rufe maganar ba don Ina gudun tozarci da tiriri na jama'a ba, nasan ni dai babu wanda zai zage ni, sunana kuma ba zai 'baci ba, na yi hakan ne kawai saboda idan maganar ta fita dole idan an rubuta sunanki za a rubuta nawa a gaba. Kuma da sauran igiyoyin aurena a kanki ba ni da yadda zan yi na 'karyata domin sakamako ne daga wajen mahukuta wad'anda suka san abin. In banda ke dashi Dr Iliyas din da ni na uku babu wanda ya san yunkurinki na fitar da cikin ta k'arfi saboda haka mu yi magana ta tsakani da Allah da annabi dake anan, na san matsayata lullub'e mini gaskiya kuwa zai iya janyo miki miki b'acin rai da fushi mai tsanani daga wurina."
Cikin dauriya da ko'karin aro jarumta na ce." Ni wannan maganar ban santa ba. Sharri ya yi mini domin neman suna a wurinka to wai akan me zan zubar da cikin da Allah Ya ba ni, me ka yi mini ko ma ka yi mini wani lefi shi cikin Ina ruwansa da zan zubar dashi, kawai Allah Ya k'addari fitarsa ne a wannan lokacin amma ni kam ban san da wannan maganar ba.

Ya gyad'a kansa yana kallona ido cikin ido sai na kasa dubansa na yi k'asa da kaina gabana na bugawa da k'arfi. Ya sanya hannunsa ya dago fuskata yana cewa." Ki rantse da girman Allan da ya hallice ki a wannan duniyar ba ki yi yun'kurin zubar da cikin nan ba Amina."
Shiru na yi ban ce komai ba zuwa wannan lokaci kuwa kafafuna sun fara rawa saboda fargaba da zullumi domin kuwa ban hangi kwanciyar hankali da yarda da kaddara daga gare shi ba.
Ya tashi ya je ya dauro alwala duk Ina zaune Ina kallonsa ya bude drowa ya d'auko al'kur'ani izu sittin ya dawo ya zauna a kusa da ni yana fad'in." Zan iya rantse miki da Allah cewa baki da gaskiya Amina, kuma bayanin da likita ya yi shine gaskiya."

Na ce." Me ya yi zafi da har sai an yi rantsuwa da al'kur'ani, kafi kowa sanin hakan babban hadari ne, kuma al'kur'ani ba abun wasa ba ne."

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

"Ban d'auko al'kur'ani da zummar wasa ba Amina, wallahi Allah daya ne kin yi yun'kurin zubar mini da ciki, ina so ki tashi ki je ki d'auro alwala ki yi yadda na yi ki d'auki al'kur'ani ki dora a saman kanki ki rantse da Allah muddin ki ka yi haka wallahi zan aminta dake d'ari bisa d'ari."
"Zan yi dai alwala amma ba ni da hurumin rungumar al'kur'ani domin ba ni da tsarki, ko ma ina dashi ni ba zan yi wannan gangancin ba gaskiya."
Ya jima yana kallona kafin ya furta." To na ji ki ba ni amsa me yasa ki ka rufe mini samuwar cikin ba ki gaya mini ba."
Shiru na yi ina d'an duban yatsun hannuna kafin na ce." Babu wani dalili mai k'arfi na bari ne kawai idan ka zo garin sai ka gani da idonka, kuma anti Yagana ta ce mini hakan kuskure ne don Allah ka yi ha'kuri."

"Ba ha'kuri na ce ki ba ni ba Amina gaskiya na ce ki gaya mini, tun muna mu biyu dake a d'akin nan idan kin yi mini gardama zan sanar da 'yar uwarki sannan na gayawa Mahaifiyata abinda ki ka yi mini na zalinci da ha'inci."
Na zuba masa ido da yanayi na damuwa na ce." Na gaya maka gaskiya baka yarda ba to karya kake so na yi maka, zalinci da ha'inci kamar yaya? wai me zai sanya ni na zubar da cikin ne ai ba shege ba ne, na sunnah ne akan wane dalili."
Cikin zafin nama ya tashi tsaye a fusace! "Ai kin shegantashi tunda ki ka zubar mini da shi, Allah Ya isa tsakani na dake ban yafe miki ba Amina."
Ya fad'a jikinsa na karkwarwa idonsa ya kada jajawur.
Tsaye na mike ni ma jikina ya fara 'bari
da yanayi na ko'karin kare kaina na ce." Menene abin Allah Ya isa, shikkenan 'kaddara ba za ta faru ba sai a jingina mini ita, ai musulma ce ni nasan abinda addini ya koyar ko cikin da ba a same shi ta hanyar mai kyau ba haramun ne zubar dashi balle wanda aka same shi ta hanyar halak, ban ga dalilin da zai sanya ku dinga kokarin dora mini lefi b......Ban 'karasa ba ya kawo mini hari na 'barin makauniya a kuncina sai na yi kasa da mugun sauri har sai da kafata ta gurde na kusa fad'uwa saboda dama jikin babu kwari ga kuma fargabar da ta yi mini dabaibayi.
Lamarin da bai taba ratsa tsakaninmu ba ko da wasa bai tab'a yun'kurin kai hannunsa jikina da zummar duka ba.
Jikinsa na rawa yake ce wa." An jingina miki lefin, ai ba ki da imani kuma baki da kyawun zuciya Amina, ke din muguwa ce mara tsoron Allah na jima da sanin za ki iya aikata abinda ya fi haka akaina tunda baki zaune da ni da zuciya daya. Ki bar ganin kina cikin hali na lalura hakan ba zai hana ni na huce takaicina ba. Abinda nake nema ruwa da iska rani da damuna na samu

har guda biyu kin zubar mini me na yi miki Amina Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!"
Ya kai 'karshen maganar da kiran sunan Allah kafin rigijib ya zube a kan gadon ya rufe fuskarsa da tafukan hannayensa gabad'aya yana nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! da baban sauti.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta

izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*29*
Ina tsammanin Hajja ce ta yi masa maganar tafiyarmu saudiya domin ni ban samu kofa ba tunda ban ga fuska. Kwanan Hauwa biyar da tarewa ya kira ni a waya, lokacin ina bandaki ina wanka, na ji ringing har sau biyu kwata

kwata ban tsammaci shi din ba, domin kafin shigata bandakin na kira Anti Yagana a waya ba ta daga ba, sai nake tunanin ko itace ta kira.
Ina fitowa na dauki wayar ina dubawa wanda ya yi daidai da lokacin da ya sake kira na dan ji faduwar gaba kad'an dalili na san ba kasafai yake kar'bar uzuri idan ya kira waya ba a daga ba.
Cikin nutsuwa nasa a kunne kafin na ce komai a hasale ya furta." Kina ina ne ina ta kiran waya."
Na tausa harshena na ce." Wanka nake yi."
Tsaki ya ja wanda ya ta'ba mini zuciya sosai, tunda nake dashi bai ta'ba yi mini tsaki ba, sai yau don kawai ban daga waya ba, a ganina tsaki yana daya daga cikin nau'ika na wulakanta mutum, kuma wata'kila tana zaune a kusa dashi ya yi mini haka.
Raina ya 'baci sosai zafin zuciyata ya motsa na dinga ji kamar na kashe wayar ma domin ban san wane kalar wulakanci zai yi mini a gaba ba.
Ya ce." Hajja ta yi mini magana akan tafiyarku jibi na ce ni ba ki gaya mini ba, ban sani ba ko kina da wani mijin bayan ni kin gaya masa."
'Kafafuna ne suka dinga kyarma jin maganar da ta fito daga bakinsa sai na ji wani gumi ya yanke mini kamar ba daga wanka na fito ba. Gabana na bugawa cikin kaduwa da furucinsa na ce" Ban gane abinda ka ke nufi?"
"Kin ji abinda na fad'a ai ba sai na maimaitamana ba, ba ni da wani mutuncin a wurinki, da ni da banza duk daya."

Na ce." Ka ga Baba,  har yanzu ban fahimci inda maganarka ta dosa ba, in banda neman fitina kai ka ba ni kujerar nan ba tare dana roka ba, haka zalika kuma ka fini sanin yaushe ne tafiya, to me zai sanya haka kawai saboda kana jin haushinsa ka nemi daga mini hankali. Me nayi maka?ka jima kana zargina saboda kawai ka aureni bazawara baka tauna magana motsi kad'an zan yi sai ka mayar da abin wata manufa, idan ka gaji da ni kana da dama a hannuna fa."

"Ki zage ni kin ji ko, ai fitsara da rashin kunya ba sabon abu ba ne a wajanki Amina, kowa yana shura ya gagara ta fannin alheri amma ke duk wanda zai bude bud'e baki aibunki zai fad'a. Ina so ki sani wallahi tallahi ba zan juri wannan sakarcin ba, ba zai yiwu da mutuncina da k'imata a gari ki zubar mini da ita ba."

Na danne kukan da yake so ya kufce mini na ce." wani abun kuma aka ce maka na aikata? wannan cin mutuncin ya isa haka Baba, ko namiji ka kama ni dashi iyakacin abinda za ka yi mini kenan, idan ba ka sona yanzu don Allah kada mu 'batawa juna lokaci mu rabu cikin mutunci ba sai ka kayi mini 'kaharu ba."

Kashe wayar ya yi ba tare da ya sake ce mini komai ba. Na ajiye tawa wayar a gefena tare da  rufe fuskata da tafukan hannayena kuka mai karfin gaske ya k'wace mini.

Cikin rashin kuzari na dubi wayata da na ajiye lambar anti Yagana ce. Sai zuciyata ta sake karyewa hawaye ya cigaba da zuba. Cikin kuka na daya jin yanayin muryata ya sanya jikinta yin sanyi a hankali ta ce." Menene kuma? Ina ce magana ta mutu tunda maigidanki da kansa ya fito ya wanke ki a idon jama'a, kukan kuma na menene?"
Na ce." Anti Yagana kisan mummuk'e yake yi mini wallahi na rasa gane inda ya dosa, ai kin ga dai ya fito ya nunawa duniya girma da matsayina, amma wallahi duk wannan k'aunar da kulawar a yanzu babu ita, a tsukin nan cikakkiyar gaisuwa bata wanzuwa a tsakaninmu abinda ya fi daga mini hankali yawan zargina da yake yi, motsi kad'an zai canza mini manufa, kin ga zargi a cikin aure haramun ne."

A sanyaye ta ce." Sai fa kin yi hakuri a wannan lukutan kin kawar da kai gefe guda, kin ki ji, kin ki gani, tunda yana da sabuwar amarya, ke ma kuma kishi yana damunki Amina, Ina ganin shine abinda ya hana ki zaman lafiya da mijinki."

"Wallahi anti Yagana ba wannan ba ne, nasan ina jin babu dadi a raina amma ya zan yi, bayan Hauwa zai iya auro wasu mu zauna, wulakancin da ya tsiro dashi ne ba zan iya jura ba."

"Amina ki yi hakuri na gaya miki, matsalarki ba ta kai wadda za ki tayar da hankalinki ba, mijinki yana sonki yayin da ya gama d'okin amarya komai zai sake shi, ke dai ki cigaba da kyautata masa kuma ki godewa Allah mahaifiyarsa tana k'aunarki to duk abinda za ki ga ni a wannan lokacin ki daure ba zai dawwama ba."

Shiru kawai na yi Ina jinta, na san ba don komai take kafe ni a gidan ba, sai dan gudun lissafin aure, yadda na san halinta hakan ta san nawa, ina da hakuri amma kuma duk ranar dana furje babu mai iya tankwarani, kuma idan na bar abu na bar shi kenan har abada.

Ta ce. " Kina jina ko Amina." Na ce." Ina jinki Anti Yagana. Sai ta cigaba da cewa." Akwai bikin da za a yi na yar gidan Babanmu Auwalu 'dan autan su Dada zai aurar da yaranshi uku maza biyu mace daya, shine Dada ta ce a sanar miki sabon watan da zamu shiga in sha Allahu."
Na ce." Zan gayawa maigidan, in sha Allah na san dai ba zai hana ba, dama kiran da na yi miki d'azu zan gaya miki za mu je umara ni da Hajja jibi in sha Allahu zamu tafi."
Ta ce." To kin ga kin samu dama sai ki tsananta da addu'a akan komai, dama kuma ita rayuwar duniya haka ta gada yau dad'i gobe kuka, ki godewa Allah kaddararki mai kyau ce."
Na ce." In sha Allah Anti Yagana a gaishe mini dasu Fadila da kyau.

Tunda na yi waya da Anti Yagana na ji sasaauci a cikin raina, na kuma yi kokarin danne abin a cikin zuciyata, domin na tabbatar da cewa Hajja ta fahimci damuwata ran kowa sai ya 'baci har shi maigidan.

Satinmu uku a saudiya ni da Hajja muka dawo. Tun ina can hankalina yake kan Yusi domin kuwa zuciyata gabad'aya bata aminta da matar gidan ba.
Duk yadda nake zaton ganinsa a firgice sai kuma na ga akasin haka lafiya lau na same shi har da 'yar ki'ba ya kara.

Ko ban ce Allah Ya bi mini hakkina ba nasan zai bi mini domin na ci wuya wurin rubuta wannan  labari yar uwata yi kokari ki sauke hakki muddin kina karanta mini littafi ba ki biya ba.

Nan na fahimci azancinta kishi da kisan mummuke akaina ne, amma bata ta'ba nunawa akan yaron ba, a wasu lukutan ma idan ya zo ya same mu a falo har jansa da wasa take yi shi ma da yake d'an gari ne anti ya kira kiranta.
Ranar da muka dawo na fahimci ya zama d'an dakinta sosai domin magana daya zai ce mini anti ta yi mini kaza ko ta ba ni abu kaza.
Ban tambaye shi maigidan ba, domin jiya da daddare kafin mu taso mun yi magana ta chart ya ce mini zamu dawo mu iske baya gida zai shiga Kano kuma zai kwana biyu.
Ban nuna damuwata ba domin ban sanya a raina cewa lallai sai ya yi murna da dawowata ba, abinda nake bashi kafin tafiyata yana da wadda take bashi a yau na kuwa tabbatar da cewa baya cikin bu'katuwa. Dama tun kafin tafiyata na cirewa zuciyata da gangar jikina sha'awarsa shiyasa idan za mu had'u ban cika kallonshi ba, wanda a lokacin da muke shiri kallansa kadai kan iya jefa ni a wani yanayi balle hancina ya ji kamshin turaransa da wannan ma yana jan ra'ayina sosai.  Raina na cire a kansa ba wai don ba na jin sha'awar ba, tana motsa mini sa'i da lokaci na kan danne ne kawai tunda na kudire wani abu a raina.
Kwanansa biyu kamar yadda ya fad'a ya dawo. Kadaran kadahan muka gaisa da juna kamar wasu abokanan gaba, amma na ji dadi da Hajja bata fahimci akwai wani abu a tsakanina dashi ba.
Yadda bai nemi ba haka ni ma ban neme shi ba duk da nasan dole ne girki ya dawo hannuna ranar kuma ni zan kwana dashi
Kwana biyuna suka tafi a banza Hauwa ta kar'bi nata .
Tsayin sati Hajja ta kara a gidan na mu kafin ta fara haramar tafiya gida, ban so tafiyarta ba amma ta kafe a cewarta dama ba ta yi mini alkawarin zama dindindin ba.
To har dai Hajja ta tattara kayanta ta koma kano gidanta na Danbatta ba fahimci komai ba dalili a tsukin kwanakin ba kasafai yake zama a gida ba da daddare kuma kafin ya shigo ya shige d'aki ta kwanta.
Yau saura kwana shiga bikin da anti Yagana ta gaya mini, kuma har ga Allah Ina son zuwa ko babu komai zan shiga cikin 'yan uwa na yi walwala ko zuciyata za ta yi sanyi.

Ba magana muke yi ba don na lura 'kebe kaina da na yi ya sosa masa zuciya sosai, ya kuma ji ciwon rashin zuwana dakinsa shiru kawai ya yi mini.
Na dinga tunanin hanyar da zan bi domin na gaya masa.
Rashin lafiya 'karya na 'kirkira, na kwanta yini guda ban fito ba. Yusi ya dawo daga islamiyya ya gan ni a kwance ya fara tambayata sai na ce masa kaina ne yake ciwo.
Jikinsa sai ya yi sanyi ya zauna gefena yana yi mini sannu yana ta tattaba wuyana wai na tashi nasha magani, don ya kyaleni na ce masa nasha d'azu da rana .
Ya'ki ya matsa ko'ina ko massalaci bai je ba, tare muka yi magariba da Isha'i a d'aki.
Misalin takwas da rabi aka murda kofar d'akin aka shigo.
Hauwa ce cikin kwaliyya har yanzu dai tana cancarewarta irin na amare.
Mamaki sosai ya kama ni, na tashi zaune Ina kallonta. Yusi kuwa fuskarsa ta fadada da fara'a tun kafin ta k'araso yake fad'in." Anti."
Ta saki fuskarta tana amsawa ta d'an dafa kafad'arsa tana kallona da murmushi a fuskarta take cewa." Amina barka da dare."
" Barka dai na furta a takaice domin ni ba yarinya ba ce balle ta ce zata nuna bariki kar nake kallonta, kuma ba wai ta samu dama ba ne, kawai na kyaleta ne saboda ni ma ina ji da tawa da mijinta ina so ya shiga gonata ne kawai.
Ta ce." Yau tun safe ba ki fito ba, ban kuma ji motsin Yusi ba dukda yau asabar nasan yana tahfiz amma idan ya je sama wajan babansa ya kan leko wurina mu gaisa har musha hirar Kamalu."
Na dubeta a tsanake na ce." Ba na jin dadi wallahi tun bayan dawowarmu zazzabi yake damuna."
Da d'an alhini a tattare da ita ta ce." Amma Kuma sai ki yi shiru, ai da kin gaya mini sai na baki magani."
A sakarce na kalleta ina jin kamar na bugeta da mari, saboda ba ni da lafiya sai na gaya mata tunda ita nake aure......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE.*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram.Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700

CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ƙano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*

*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*36*
Ta 'bata rai tana ce wa." Matsalata dake taurin kai Amina, kishiyarki wallahi ba a zaune suke ba, babban burinsu ki fice ki bar gidan, kin ga idan ba ki ba ni goyon baya ba sai na yi asarar kudina dubu arba'in na fitar aka ba ni turaran nan da kuma wannan rubutun."
Na cika da mamakin jin kudin da ta bayar har dubu arba'in lallai anti Yagana ta d'auki lamarin nan da girma, ai idan dan ta ni ce wallahi ba wani yawon neman taimako da zan yi a ci kudina a banza. Na tabbata anti Yagana bata ta'ba zuwa wurin wani malami ba sai akan matsalata hakan ne ya sanya na amince zan yi amfani da maganin amma da sharad'in ko da bai kira ba to ba zata kira shi ba domin ta ce mini malamin ya ce idan bai kira ba to sai a kira shi.
Ta amince da abinda na ce ni kuma na kar'bi rubutun da turaran a take a lokacin na fasa daya nasha ba tare da yakini ba.
Da kanta ta je ta hura wuta ta ruru sosai ta shigo da garwashin da yawa a cikin kasko irin na kasa ni dai kallonta kawai nake yi ina mamakin yadda ta d'auki al'amarin.
D'aki ta nufa da rushin wutar kafin ta kwalo mini kira na tashi na je na sameta tana kwance ledar turaran, ta ce." Sai kin cire kayan jikinki tsaf sai ki rufa da wannan zanin, amma idan kin zuba turaran akan wutar sai ki dinga yi kina kiran sunansa.
Fashewa na yi da dariya na fadi saman gado ina kyakyatawa domin duk yadda na kai ga son ganin na danne dariyar kasawa na yi.
Ta yi kasa'ke da ledar maganin a hannunta tana hararata. Ni kuwa Ina dariyar na ce." Wallahi anti Yagana dariya kike ba ni, wani irin turare ne wannan da

har sai na yi tum'bur haihuwar uwata, na rantse da Allah malaman nan suna nema su jefa mata a masifa."
Ta sha kunu tana cewa." Kina d'auka abin nan da wasa ko Amina, nema ma ki ke yi ki mayar da ni mahaukaciya saboda baki da mutunci ko ina tsaye akanki amma ki sanya ni a gaba kina yi mini dariya ba za ki fahimci abinda nake nusasheki ba sai ranar da ma'kiya suka kai ki 'kasa tukkuna."
Ganin yadda ranta ya 'baci ya sanya na tashi zaune sosai na kar'bi ledar da turaran yake daure Ina fad'in." Zan yi yadda ki ke so anti Yagana"
Shiru ta yi mini tana cigaba da wurgo mini harara. Babu yadda na iya da ita haka na tashi na fara cire kayan jikina, ya rage daga ni sai rigar mama tana tsaye tana kallona na dubeta tare da cewa." Ko suma din na cire su?"
Ta girgiza kai." Ki bar su kawai ai."
Ban sake cewa komai ba na zuba turaran akan wutar lokaci guda hayakin mai kauri ya tashi na yi sauri na rufa zanin ajikina na dukufa kan wutar ita kuma da sauri ta kama hanyar fita tana fad'in." Kada ki manta ki dinga ambaton sunansa fa."
Na ce." To shikkenan."
Ina jin karar jan kofarta na cillar da zanin na tashi daga kan wutar na matsa gefe ina haki da tari ya sarke ni.
Hayakin ya cigaba da bin iska ina gefe guda. Na ji motsin bude kofarta a guje na d'auki zanin na je na dukufa kan wutar ta leko tana cewa." To kin ga haka ai ya fi, kin shaki hayakin sosai, in sha Allahu da izinin Allah zai kira waya yau din nan sai a daidaita, malamin ma cewa ya yi hakuri zai bayar."
A zuciyata na ce.'' Anti Yagana da tun farko kin k'adaita Allah ba za ki nufi wajan wani malami ba, suma duk hasashe suke yi.
To haka muka yini muna tattauna sha'anin Hadiza da abinda ta aikata, ni ma yanzu na dawo daga rakiyar Ummansu domin ta zama bakin ganga na yarda itace take dorata a gwadabe mara kyau amma duk lokacin da zata kira ni a waya nuna mini take yi itama Hadizan tafi k'arfinta ha'kuri take da halinta a zahiri kenan amma a bad'ini bakinsu d'aya. Na riga na gama fahimtar cewa Hadiza da ni take gasa tun daga kan mutuwar aurena kawowa yanzu burinta itama ta tara arziki har ta kere mini.
Tun bayan sallar Isha'i na lura da anti Yagana jikinta ya yi sanyi duk wani abu da take yi babu kuzari domin abincin dare ma ni na yi mana towon samovita miyar ku'bewa tun yamma take ce mini jikinta yana ciwo dalilin da ya sanya kenan tasha Panadol ta kwanta amma dai karin kasalarta yana da ala'ka da dakon kiran wayar Alhaji Tajo domin yadda na fahimta ta gama aminta da abinda malaminta ya gaya mata.
Muna d'an ta'ba hira sama-sama Babandi ya zo, bai samu wata tar'ba ta arziki ba a wajan matar gidan anti Yagana kenan, ni kaina daurewa kawai na yi nake tanka masa amma duk da haka babu cikakkiyar sakewa kamar yadda muka saba,  ina jin hakan da ya fahimta ne ya sanya shi yi mana sallama ba tare da ya shirya tafiyar ba domin idan dai za mu had'u muka shafe sama da awa biyar muna hira ba tare da gajiya ba, yanzu kam ko minti talatin bai yi ba ya kama hanya ya tafi ba karsashi a tare dashi.

Anti Yagana ta rakashi da tsaki da harara duk ina kallonta ban ce mata komai ba.
goma da wani abu Babansu Fadila ya shigo ita lokacin ta shiga d'aki tana kintsawa.
Ya tsaya a falon muna dan ta'ba hira da yake akwai sabo a tsakanimu dukda wani sa'in idan na zo garin har na kare kwanakina bai fi sau biyu muke had'uwa dalili shi din babban direba ne kuma yana da muk'ami a tashar da suke ajiye motocinsu da asuba yake fita sai dare yake dawowa kamar i yanzu.
Ya tsaya yana tsokanata da fad'in." Ranki ya dad'e ina kamun 'kafa fa, a cewa maigidan a irin wad'annan motocin nasa muna neman koda guda d'aya ce wadda za mu dinga lodi daga nan kudu, idan haya ake bayarwa a taimaka a ba mu, idan kuma za a ba mu ne sojan haya zuwa shekara biyu in sha Allahu sai mu mayar da kudin, dama tuntuni nake so na samu dama na bi ta karkashinki, kwanaki an ce mana ya rabawa direbobi biyar kuma uku daga ciki ma an ce kyauta ya basu ba mutum biyu ya kar'ba."

Tsakaninsa da Allah yake gaya mini babu wasa a cikin maganar. Ganin haka ya sanya ni ma na shiga nutsuwata na ce." Aikuwa ban san kana buk'ata ba wallahi tabbas watannin baya na ji yana maganar da wad'anda Allah Ya sa suna da rabo, amma in sha Allahu kuwa zan yi masa maganar idan na koma duk yadda muka yi dashi sai na sanar da kai."
Da farinciki mai yawa ya fara godiya har da kirari kamar wani maroki na dinga dariya ina zolayarsa da cewa sharad'in idan na yi masa hanya ya samu babu shi ba kara aure fad'i yake yi." Na yarda ai tuntuni na gaya mini Yagana ta rufe kofar kece ba ki yarda ba."

Dariya kawai na yi domin nasan yana fad'a ne kawai amma ba har zuciya ba, babu wani namiji da zai so ya rayu ya mutu da mace daya yawancinsu suna ha'kura ne saboda wasu dalilai amma an riga an hallicesu da son mata wannan a jininsu yake akwai ma mazan da suke da tarangahuma sun yarda su tara matan duk abinda ma zai faru sai dai ya faru. To wad'annan sune za mu kira da masu rashin tsinkaye da hangen nesa.

Ki biyaa ni hakkina kafin ki karanta mini littafi yar uwa akwai hakkina akan ki domin littafin nan na kudi ne.

gajiya na yi da tunani na tashi na je na kwanta wanda bacci da k'yar ya d'auke ni. Misalin shida da rabi wayar Hamusu ta tashe ni daga b'ingirewar da na yi bayan sallar asubahi
Muka gaisa sosai dalili mun kwana biyu ba mu gaisa ba kamar yasan maigidan yana adawa da hakan a tsukin ya rage kira na a waya sai dai ya turo mini da voice note ta whasap. Ni ma sai na fi jin dadin hakan. Nan yake gaya mini Gwaggo ce bata da lafiya dalilin da ya sanya ya kira ni domin jikin nata ya fara tsanani.

Cikin kankanin lokaci na ji hawaye ya cika kwarmin idona. Gabad'aya sai na diririce hankalina ya tashi sosai, na ce." Hamusu ina nan maiduguri na zo bikin yaran d'an'uwan Dada, ita Gwaggwon za ta san shi tunda tare suka taso. Amma zan yi kokarin d'auko hanya gobe yadda kake fad'in jikin nata hankalina ya tashi sosai wallahi, ina fatan kun kai ta asibiti.
Ya ce." Kiran da na yi miki kenan, domin babban asibiti nake so mu kaita su bata gado sugar ne da hawan jini, mun je asibitin murtala likita ya dubata ya rubuto magani an Siya kwana biyu an samu sau'ki wallahi jiya kuma sai ta tashi bata iya motsa komai a jikinta, kuma ba damar na yi amfani da kudinki ban gaya miki ba "
Raina ne ya baci jin abinda yake fada. Na ce." Hamusu wannan wace irin magana ce, ashe akwai ranar da za ka iya nuna mini cewa Gwaggwo ba ta haife ni ba, kudin nawa wanene yake juya mini Ina ce kaine jigo har sai ka tambaye don za ka kai Gwaggwo asibiti wallahi baka taba ba ni haushi ba irin yau."
Ya ce." Ki yi hakuri anti Amina ta wani gefan fa Ina da gaskiya, kudi suna iya shiga tsakanin kowa shiyasa sanarwar take da amfani."
Na ce." Ka ga malam maganar ta isheni haka don Allah, ka je daga dubu daya zuwa dubu dari biyar har abinda ya yi sama na amince muddin akan gwaggo ne. Sai ya fara godiya ban jira na saurari sauran maganar ba na datse kiran na fita falo.
Anti Yagana tana kicin tana aikin karin kummalo Fadila tana taimaka mata
Yusi da sauran yaran sun fito bakin famfo suna ta burush da wasa da ruwa.
Na dan jingina a jikin bango a sanyaye na ce." Anti Yagana mun tashi lafiya ya hidima?"
Ta amsa hankalinta yana kan abinda take yi, na ce.'' Ina ganin gobe asubanci zan yi zuwa kano Gwaggo bata da lafiya yanzu nan Hamusu yake gaya mini jikin nata sai a hankali."
Ina dire maganar da take bakina Yusi ya zo ya tsaya da burush dinsa a hannuna.
Anti Yagana cikin alhini ta ce." Allah sarki Gwaggwo ciwon har ya kai ace bata san wanda yake kanta ba, kenan tana asibiti a kwance."
Na ce." Ina fa, tana gida saboda shashancin Hamsu bai gaya mini ba har sai da ciwon ya ci k'arfinta wai ya kaita asibitin murtala da farko yanzu kuma abin yayi tsanani shine fa ya kira ni yake gaya mini da abin haushi wai yana neman izini zai yi amfani da kudina.
Ta ja tsaki tana fad'in." Wauta da rashin hankali shikkenan don ya d'auki Gwaggwo ya kaita asibiti da kudinki sai ki ce masa don me, ya ba ni haushi wallahi."
" Wallahi ni ma ba ki ji yadda raina ya baci ba wannan ai shiririta ce rashin lafiya ya wuce komai, kuma ko dukiyata zata kare akan nemawa Gwaggwo lafiya anti Yagana wallahi ba zan damu ba"
Ya girgiza kai tana cewa." Kwarai kuwa ai Ido ba mudu ba ya san kima."
"Mama wai Gwaggo ce bata da lafiya?"
Na dube shi ya zuba mini ido da yanayi na damuwa a tare dashi.
Na ce." E, itace amma jikin da sauki alhamdulillahi."

A sanyaye ya ce." Mama idan za ki je zan biki don Allah....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky
*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*

*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*
*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*38*
Hanyar fita na kama na ji muryarsa har tana rawa yana ce wa." Mama ki gaishe mini da Gwaggwon."
A takaice na ce." Za ta ji in sha Allahu. Na yi saurin ficewa da addu'a d'auke a bakina.
Ina fita harabar gidan na ci karo da Sukairaju zaune a bakin kofar masaukinsa yana waya. dauke kaina na yi, na sake hade raina sosai. Ido ya zubo mini Ina kallonsa ta gefan idona. Ban tanka masa ba na kama hanyar fita sai ya taso da sauri ya biyo bayana da wayar a kunnansa da maigidansa

yake waya saboda yadda yake yin kasa da murya cikin ladabi kamar yana kusa dashi.
"Ranki ya dad'e barka da asuba."
Muryarsa na ji a daf da ni, na juya ina dubansa yana biyo bayana da wayar a hannunsa..
A takaice na ce" Barka kadai Sukairaju ya kake?"
Ya ce." Alhamdulillahi, idan ba matsala Ina iya yi miki rakiya don yanzu muka gama magana da oga ya ce na biyo bayanki."
Cikin jin haushi na ce." Makauniyace ni, da za ka biyo bayana ko kuwa ban san gari ba."
Ya girgiza kai cikin ladabi ya ce." Ko daya kulawa ce da kuma bin umarnin maigida."
Na ce." To ka kira shi ka gaya masa na ce ba na son kulawar wannan wace irin masifa ce ne ."
Sai ya tsaya ya yi sararo. Na ja tsaki na fara tsayar da abin hawa shi kuma ya fara laluban wayarsa da sauri ya kara a kunne yana cewa." E to ga mu nan ni da ita atare a bakin titi tana tsayar da mashing tana tare da k'aramar akwati."
Ina jin sautin muryarsa amma ban ji abinda yake cewa ba. Daidai lokacin adaidaita sahun dana tsayar  ta yi parking na yi saurin shiga. Shi ma da sauri ya zagaya ya zauna kusa da direban shi kuwa ya ja babur din ya hau titi.
Takaici kamar ya kasheni, ni wulakata mutum ba dabi'ata ba ce, kuma ba na so na fara akan mutumin nan tunda na lura shi ma yana gyara hanyar abincinsa ne, kuma duk umarnin da aka bashi dole ya bi.
Ban ce masa komai ba har muka isa tasha na fito, shima ya fito da kudi ya biya direban ya zo yana ko'karin kar'bar akwatin hannuna.
Na ce." Kira mini ogan naka a wayarka."
Da sauri kuwa ya fito da wayar daga gaban aljihunsa ya kira shi ya miko mini wayar kafin ya daga na matsa can gefe wajan da babu hayaniya sosai duk da safiya ce amma tashar cike take da jama'a.
Yana d'agawa ya fara da cewa." Sukairaju ya aka yi, na gaya maka duk inda ta sanya kafarta ka ajiye taka anan ka kula sosai da ka ji ko?"
Na ce." Bashi ba ne ni ce Amina."
Ajiyar zuciya ya sauke ya furta a Ina ki ka ajiye wayarki ina kira baki daga ba." Lokacin da ya kira tana cikin handbag d'ina kuma na ji kiran ina sane ban daga ba.
Na ce." Tana hannuna wayar ba ni da lokacin d'agawa ne."
"Okey na ji, ina za ki je da sanyi safiya haka harda akwati kin san duk inda ki ka nufa ba ki tsira ba tunda da aurena a wuyanki."
"Shiyasa kenan ka bada tsarona saboda kada na gudu yawon bin maza ko."
Shiru ya yi bai tanka mini ba. Na ce." Idan kana kan layi to don Allah ka umarci wannan gardin da yake bina a baya ya koma, ko kuma ya tattaro ya dawo karkashin aikinka dan banga amfanin zamansa a gidan mutane ba face dora musu nauyi da ya yi, domin ni na gaya maka ban mayu ba har abada zama ya kare a tsakaninmu."

Hankalinsa a kwance ya ce" mutan gidan ne suka ce miki sun gaji dashi saboda yana dora musu nauyi ko kuma sharri ki ka yi musu."
Da sauri na tari numfashinsa ." Sai sun fad'a sannan za a gane yanayin rayuwa ya za a yi baligin mutum kamar wannan ka zo ka ajiye shi a gidan mutane da sunan bada tsaro akwai wani tsaro ne wanda ya wuce wanda Allah yake ba ni tun kafin a haife ni."
"Zan kira anti Yaganar na ji shin cewa da yawunta ne ki ke fad'in hakan, na san halinta da karamci ba za ta ci zarafin bako ba."
Jin abinda ya ce sai jikina ya d'an yi sanyi nasan halinsa tsaf zai iya kiranta ya tambayeta.
Kashe wayar na yi ban tsaya saurarar abinda yake cewa ba.
Kafin na mikawa masa abarsa ya kara kira na daga wannan karon cikin tsare gira da kaurarriyar muryar da babu wasa ya furta." Ki gaya mini Ina ki ka nufa yanzu domin na ji hayaniya da karar ababan hawa hala kina cikin tasha ko?"
Na ce." Eh ina tasha zan nufi kano domin duba jikin Gwaggwo da izinin Allah, zan kuma biya na gaishe da Hajja."
Ya sassauta yana fad'in." Na amince dai ki je ki duba Gwaggwon amma ban amince miki zuwa wurin Hajja ba, ke kwata kwata ma ba na so asan kin shiga garin, ki zauna a gidanku kawai kwanaki biyu zan gama yi muku shiri sai ku biyo jirgi ku dawo gida ga'badaya."
Na ce." Gaskiya ba zan iya shiga garin kano ban je wajan Hajja ba sai da ka yi hakuri.'' Kai tsaye na fadi hakan domin a karon farko na fahimci akwai abinda yake b'oyewa dama na san duk abinda yake faruwa ba ta sani ba."
Ya sake sassauta murya cikin sigar rarrashi ya ce." Na ji kije amma kada ki gaya mata duk abinda ya faru tsakaninmu sanin kan ki ne bata da lafiya."
Na ce." Ai ta inda aka hau ta nan ake sauka Yallabai, ai ba auran 'yar tsana muka yi ba sai da waliyyai da shedu suka shaida to me zai sanya kuma a boye musu saki yana da kyau ta sani yanzu saura igiya biyu."
Diriricewa ya yi ya fara fad'in." Ki saurare ni ki ji, na gaya miki wallahi muddin ki ka sanar da Hajja wani abu sai na sa'ba miki, kin ji na gay......Datse wayar na yi Ina jin wasai a cikin raina na tabbata ta wannan hanyar ma kadai zan hukunta abina.

Ya yi ta kiran wayata ban daga ba, da ya gaji sai ya kira ta yaron nasa, kimanin minti goma suna magana kafin su gama wanda ni lokacin ma na gama da wani direba inda na d'auki shatar mota guda na biya..
Ya k'araso yana tambayar direban yadda muka yi duk ya gaya masa ai na riga na biya ba tare da ya dube ni ba yake gayawa direban tare za mu tafi.
Na dubi direban ina fad'in.'' Ni da na biya ka kudin motar umarnina zaka bi ko nasa."
Cikin ladabi ya d'an risinar da kansa ya ce." Ranki ya dad'e umarninki zan bi, amma yana da kyau mu tafi tare dashi tunda yana tsoronki ne kin san fuskarki da ta maigidanki ba 'boyayyiya ba ce, ni na yi mamakin ma ganinki cikin tashar nan.

Jin haka ya sanya da sauri na bude motar na shiga domin sam ban yi wannan tunanin ba yanzu abin sai ya zama magana da yayatawa kafafen sadarwa.
Na dubi Sukairaju da yake ta ko'karin sanya akwati a bayan mota na dan leka ta tagar motar a nutse na ce." Ka je ka taho da Yusi ina nan ina jiranka."
Yadda ya amsa da sauri shi ya tabbatar mini da cewa bai kawo cewa dabara na shirya masa ba.
Ina ganin ya shiga adaidaita sahu. Na dubi direban da yake jingine a jikin motarsa na ce." Ka shigo mu tafi na gama magana dashi ya koma gobe zai biyo bayana da yarona."
Ya d'an yi jim yana kallona kamar bai yarda ba, na 'bata rai tare da cewa." Ka ga idan ba za ka je zan fito na nemi wata motar menene hakane?"
Ya bude motar ya shiga ya zauna a mazauninsa jikinsa duk babu k'wari haka ya kunna motar wani abokinsa ya zo ya tsaya suka d'an yi magana kafin ya bar wajan shi kuma ya ja motar muka fita daga cikin tashar sai sannan hankalina ya kwanta.

Don girman Allah ki biyani hakkina kafin ki karanta mini littafi kada ki bar nauyin wani akanki.

Bayan mun d'auki hanya sosai na kira Hamusu domin jin a ina aka kwana nasan tunda mutumin nan ya yi ruwa da tsaki akan lamarin nan da wahala gwaggo bata kwana asibiti ba. Illai kuwa muna gaisawa ya fara da cewa." Yanzu nan da na fito daga wanka nake shirin kiranki wallahi, jiya wajan goma da rabi na samu kira daga maigidanki ya ce mini mota tana zuwa daga asibitin Malam za ta d'auki Gwaggwo babban likita zai dubata sosai. In takaice miki dai Gwaggo tana can an bata gwado kuma jiki da sauki alhamdulillahi na dawo gida domin na yi wanka, anti Amina ki kara yi mana godiya a wajansa lallai yana abinda ya dace da dukiyarsa wallahi anti Amina d'akin da aka kwantar da Gwaggo daban yake da sauran ita kadai ce ba hayaniya kuma tun jiya da daddaren likitoci suka ta zaryar shigowa dubata."
Jikina ya d'an shika kad'an jin yadda Hamusu yake yi mini bayani kamar ya fashe da kuka sai godiya yake yi. Cikin raina na ce.' Haushinka yake ji Hamusu amma saboda iya taku da neman suna ya dabaibayeka da alherinsa ta inda da wahala ka hangi kuskuransa.
Na ce." Babu damuwa Hamusu ai Gwaggwo ta wuce komai, ni ma gani a kan hanya in sha Allahu daga zarar na sauka zan kira wayarka."

Babanmu na kira na gaya masa ina kan hanya. Na kira Sahura itama na sanar da ita, daga nan sai na fara tunanin inda zan sauka, ba zan iya zuwa gidan Hajja ba gaskiya gidanmu kuma babu spece d'akin da na yi zawarci Ummansu Saminu tana kiwon kaji. Kawai sai na yanke shawarar sauka a gidana na kuntau. Yana kulle har yanzu shagon ne dai ake ta hada hada a cikinsa dama mun yi da Hamusu cewa idan auransa ya tashi zai zauna a ciki gidan to an samu tsaiko ne daga bangaran budurwar da yake nema babanta ya ce sai ta yi karatun likitanci shi kuma ya'ki ya canza wata ya dage sai ita

yanzu dai an kai kudi an sa rana shakara uku mun ci shekara daya yanzu saura shekara biyu.
Sake kiransa na yi a karo na biyu na umarce da cewa ya sanya yara su wanke gidan su gyara shi sosai, shekara kusan biyu dole a samu datti. Ya ba ni tabbacin cewa kafin na sauka za a kammala.
Koda muka isa ban fito ba saboda ina gudun idanun mutane can tsallaken titin da muke na hangi masu sayar da abaya da hijab da nikab na fito da kudi na ce wa direban ya je ya sayo mini nikab.
Ya kawo mini na rufe fuskata sai kwayoyin idona kawai ake gani. Na kira Hamusu na sanar dashi. Minti talatin a tsakani ya k'araso kan sabon babur d'insa da ya saya.
Na fito daga motar Ina yi wa direban sallama shi kuma sai risinawa yake yi. Har na hau babur din na ce da Hamusu ya dakata dubu biyar na sake bashi bayan kudin motarsa dana biya shi tun a tashar garinsu. Ya dinga godiya kamar ya ari baki, har dai Hamusu ya ja babur din ban daina jiyo sautin muryarsa ba.

Mun hau titi sosai ya ce.' anti ina za mu je ne? Gida zan kai ki ki huta ko kuma asibitin zan wuce da ke."
Na ce." Hamusu kai ni asibiti na fara duba jikin Gwaggo hankali ya fi kwanciya......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram.Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

TEEMAH DATA SERVICES MTN
1GB @550
2GB @950
3GB @1450
4GB @1550
5GB @1700
CHECK CODE *323*4#
VALIDITY 30DAYS
CHAT@08112392177
CALL @08037026306
8037026306 fatima musa ibrahim opay

https://chat.whatsapp.com/K944WIHnBaKHDrZS6snUky

*TALLAH!*
*Albishirinku mata ƴan ƙwalisa matan da suka amsa sunansu mata, waɗanda suka san sirri da fa'idar gyaran jiki domin ta da komaɗar sha'awarsu. To ku matso kusa kuji, wai kuna da labarin shahararren kamfaninnan na ƙawa da ƙawa ɗaya tamkar da dubu, sha ƙundum, mai suna?*
*DUNIYAR LAFIYA ISLAMIC NATURAL PRODUCT & WOMENS CONSULTATION*
*Daga aunty Fatima Buhari rijiyar lemo ķano state*
*Cibiyace da tai fice wajen gyaran ma'aurata*
*Wannan kamfanin basu fito ba saida suka shirya tsab domin taimakon mata ta hanyar samar musu da magunguna ingantattu nagartattu wanda aka haɗa da natural kaya cikin tsabta da inganci, komai a kwali yake ƴar uwa cikin tsabta da nutsuwa aka shirya muku*
*ina masu son soma kasuwanci ku matso Anty Fatima tana bada kaya a sari akan farashin da zaki gode mata, tana raba kayanta ga manyan shagunan saida magunguna dake cikin kasuwar kurmi dake kano, tana tura kayanta izuwa gari_gari ƙasa_ƙasa. Kayan sari kona miliyon nawa kike da buƙata zasu iso hannunki a cikin kwana biyu da izinin Allah*
*Ni Badiat Ibrahim Mrs Bukhari ƙawar Sabuwan maigogul, Aminiyar Iyabo, uwar ɗakin Tani Shanono na gwada na san amfaninshi, kema ƴar uwa ki kwada zaki bani labari siyan nagari maida kuɗi gida.*
*Mun sani yanzu yana da kyau duk abinda zamu siya musan ingancinshi da nagartarshi bawai muita siyan magungunan mata kara zube ba.*
*Wannan kamfanin kayansu babu algus ko almundahana a ciki, da tsoron Allah da ƙwarewa gami da gogewa ta sanin* *yadda ake sarrafa magunguna suke aikinsu, cikin nagarta da gangariyar tsabta.*
*Abu mafi sha'awa komai a cikin kwali yake a rufe kirib*
*ga kaɗan daga cikin abubuwan da kamfanin yake samarwa*
*Tsumin dadi har Madiga tareda gunbarshi*
*Tsumin no excuse melaƙabin bita zaizai*
*Gumbar dare daya wanka goma, dana gari da zumarta da tsuminta duk muna dashi*
*Zumar hana bacci gumbarta da garinta*
*Munada Arabian sabaya tare d Sudanese sabaya*
*Da zumarta*
*Sabaya ce dake cuko da ƴa mace duk ramarta, da ƙanjamewarta*
*Itama da zumarta*
*muna da mummuna da aiki*
*Akwai tsumi da gumbar ta da zaune tsaye*
*muna da kogin daɗi*
*Abangaren sanyi sun samar ma mata maganin matsolilinsu*
*muna da fitattun maganin sanyin da yake fata_fata d sanyi yayi mishi korar kare*
*Khanzur Rahman herbal formular*
*Sanyi clear syrup*

*7 days for chronic infections flusher*
*Sannan kuma muna da* *Package amarya*
*Package Uwargida*
*Package irin na zawarawan da suke shirin sabon aure*
*Bugu da ƙari wannan kamfani yana sarrafa magungunan maza ba a iya na mata ya tsaya ba, wannan kamfani magungunan da yake samarwa suna da yawa wannan tsakurene daga cikin kayansu*
*Da sauransu da sauransu wanda bamu ambata ba.*
*Ba fa a iya haka muka tsaya ba muna d cancada cancadan zannuwan Gado da carpet*
*Domin neman ƙarin bayani ku tuntuɓeta a kan lambar wayarta kai tsaye*
+2348032089456

*37*

Ya fad'a muryarsa har tana rawa, sai ya ba ni tausayi ni ma na ji idona ya ciko da kwalla dama daurewa kawai nake yi.

Haka muka karya a daddafe har yaran suma gabad'aya jikinsu ya yi sanyi ganin yadda muke cikin alhini da damuwa Yusi dai ya takure a kusurwar kujera har da kuka sai da anti Yagana ta rarrashi tukkuna ya yi shiru.
Garba almajirin anti Yagana ya shigo ya ajiye robarsa a bakin kicin ya shigo falon muka gaisa anti Yagana ta ce ya yi maza ya zuba ruwa a diro amma kafin nan ya fara wanke shi. Har ya juya zai fita sai ya tsaya yana kallon Yusi ya ce." Ka je in ji wannan din nan yama sunansa?" Ya tsaya yana tunani. fadila ta ce." Bak'on da suka zo tare?"
Da sauri ya daga kansa yana cigaba da cewa." E shi ya ce na kira shi yanzu ya je Babansa ya kira waya za su gaisa."
Na dubi Yusi da mamaki a tare da ni, dama duk safiya Yana kiran waya don su gaisa, da farko da Garba ya ce ya je na d'auka Sukairajun yana buk'atar wani abu ne bayan karin kummalon da aka kai masa.
Yaron ya tashi da saurinsa sai na dakatar dashi ina fad'in." Yusi dama Baban yana kiran waya ne ku gaisa kullum?"
Ya ce." E wataran ma har ya ce na bawa su Arif da Sultan su gaisa, ko Arif?" Ya fad'a yana kallonsa. Ya ce." Eh hakane har ya ce a gaishe daku bakidaya.''
Na gyada da mamaki fal a tare da ni. To shin wai me mutumin nan yake nufi ne? Ni ban ma ga amfanin zaman Sukairaju a tare da ni ba, kuma yaro dai ni na haifi abina ba za a yi wannan munafurcin da ni ba, ka sake ni amma ka dinga bibiyar 'yan uwana har da yaron da na haifa da wani namijin.
Na ce ." To koma ka zauna ba za ka je ba."
Anti Yagana da sauri ta ce." Akan me?" Shiru na yi kawai Ina kallonta da mamakin neman dalilin da take yi wanda ta fi kowa sani.
Tana kurbar kunun gyadar da ta tsiyaya kofi ta ce." Ki kyale shi kawai ya je, idan kuma ba so kike ki fito da komai fili ba, ta inda ya fi ki wayo kenan, yadda yake tafiyar da lamarin a siyasance sai ki zuba Ido ki ga iya gudun ruwansa."

Na yi shiru Ina nazarin maganarta. Ni dai da ta barni zan datse alakar ne daga yau din, shi ma Sukairajun na sallameshi don ban ga amfanin zamansa a tare damu ba illa dorawa masu gidan nauyi da ya yi."
Kimanin minti ashirin yaron ya yi da fita sai gashi ya shigo ya zauna yana kallon anti Yagana ya ce." Baba ya ce na gaya miki zai kira ki yanzu."
Da sauri ta ce." To shikkenan Yusifa."
Kawai na saki baki ina kallon ikon Allah. Gabad'aya abincin ma da nake ci sai ya fita daga raina na zuba mata ido a lokacin da ya kirata suna magana akan rashin lafiyar Gwaggwo.
Anti Yagana ta saki jiki da baki tana ta jadadda masa yadda Gwaggwon take jin jiki har da ce masa tana kwance bata iya motsa komai na jikinta.
Da yake handsfree ta sanya wayar ina jin muryarsa tar yana cewa." Ni muna gaisawa da Yusuf na ji ya fashe mini da kuka koda na tambayeshi shine yake gaya mini kakarsa ce babu lafiya kukan yaron ya daga mini hankali kwarai da gaske dalilin da ya sanya ma kenan na kira ki domin na tabbatar ya gaya mini duk yadda aka yi, zan yi waya asibitin Malam din  duk abinda ake bukata game da mara lafiyar ba zai gagara ba idan ma gado za su bata hakan zai fi sauki Allah Ya bata lafiya."
Anti Yagana tana ta amsawa da Amin Ya Allah, mun gode sosai da kulawa Allah ya kara arziki da wadata."
Suka yi sallama ta juyo tana kallona raina a tsananin 'bace na mik'a hannu dukkunsu har shi Yusi din ba su ankara ba na kife shi da marin da na tabbatar zai gigita shi .

Kiji tsoron Allah idan har kin san baki biyani kudin littafina ba to kada ki karanta zai fi miki alheri ki ha'kura ko ki biya mai hakki hakkinta.

Illai kuwa a ki'dime ya tashi ya yi hanyar waje hannunsa dafa da kumatunsa hawaye suka fara kasa tsere a kuncinsa.
Anti Yagana ta rufe ni da fad'a tana fad'in." Sai kin je kin tsiyayar masa da ruwan ido haka kawai saboda zalinci zaki kifa masa wannan mugun marin me ya yi miki? Lefin dai ba zai wuce ya gayawa mijinki magana ba, shikkenan fa sai ki lahanta shi.''
Shiru na yi ban tanka mata ba kawai na tashi da zumar barin wajan. Yaron da yake tsaye a bakin kofa ya d'auka dukansa zan sake yi ya fita a guje yana sheshsheka.
D'aki na shiga na zauna a gefan katifa kaina a daure domin duk yadda na kai ga ganin na hasaso abinda mutumin nan yake nufi a kaina na kasa ganewa.
Shin wai ko ya manta da cewar ya sake ni ne, wane irin munafurci ne wannan da neman lallai sai ya d'ora mini lefi. Ka sake ni ka fita daga sha'anina mana.
Wayata na d'auka da sauri kiransa zan yi domin na ji shin me yake nufi da ni ne.
Kamar yana jiran kiran nawa karaf ya daga. A kaurare babu gaisuwa balle girmamawa dalili duk ya zubar da mutuncinsa a idona bana son mutum munafiki.

Na ce." Ban gane abinda kake nufi ba, ko ka manta cewa yanzu babu wata alaka da take tsakanina dakai? Ina ruwanka da bibiyar abinda ya shafe ni. Gwaggwo dai mahaifiyar mijina ce wanda mutuwa ta yi mana kutse ta shiga tsakani, na tabbata kuwa a duniyar nan ba zan sake katari da namiji mai nagartarsa ba. Kana ta bina da sharri, ka yi nan ka 'bata ni, ka bi nan ka 'bata ni, to ta Allah ba taka ba, ka ja tsumman rayuwarka, ba ma buk'atar ko kwabonka, ba na son munafurci ni."

Cikin nutsuwa kamar bai ji zafin maganganuna ba ya ce.'' Ai na mayar dake dama na yi ne domin ya zama gargadi a gare ki. Kuma ba don ke nake tsaye akan abinda ya shafeki ba, saboda wasu dalilai ne, ke ki ka haifi Yusuf amma ya fi ki hankali, kuma saboda shi  din na shiga lamarin, ai na san kakarsa ce ko ba itace ta haifi Aminu Salihi ba."
Cikin takaici da b'akinciki na furta." Ban mayu ba, wallahi ban mayu ba na saku har abada ni dakai dama can ba a son raina aka yi ba, ba zaka tozartani ba wallahi ko maza sun kare a duniya ba zan zauna da kai ba, kuma ko mutuwa Gwaggwo ta yi menene abinda ya dame ka, babu ruwanka ba na son munafurci fa." Na sake maimaita kalmar munafurci domin na tunzurashi.
Bai tunzuru ba a tsanake ya ce." Sai ki yi kuma ni dai na mayar dake shekaran jiya na yi sakin jiya da safe kuma na kudire a raina na mayar dake yanzu kuma na sanar miki, don haka har yanzu kina karkashin ikona."
 Da sauri ya yanke wayar kamar ya san abinda yake bakina mai muni ne tabbas da bai kashe wayarsa ba sai dai ya ji ruwan ashar a kunnansa  saboda yadda zuciyata take a tunzure. Na kasa motsi daga inda nake gumi na yanko mini tsabar tashin hankali kamar yadda ya fad'a a musulunce na mayu tunda ko jini daya ban yi ba kuma ka'idar musulunci jini uku ne na fita daga idda.
Hawaye masu zafi suka fara karakaina a kumatuna. Anti Yagana ta shigo d'akin da karsashinta ganin yanayin da nake ciki ya sanya ta d'an yi sanyi ta tsaya tana fuskantata..."Menene kuma?" Tambayar da ta yi mini kenan.
Cikin k'unci da takaici na ce." Anti Yagana a wannan karon dole ki yi hakuri na d'auki mataki da kaina domin siyarwa kaina mutunci. Yadda na lura da mutumin nan bashi da mutunci ko kad'an kuma yana yi wa mata kallon wulakantattu idan ba haka ba me zai sanya ka saki mace haka kawai babu hujja mai karfi saboda kawai jin dadi gobe kuma ka ce ka mayar da ita addinin bai ce haka ba Anti Yagana ki zauna ke kanki ki dubi lamarin nan a tsanake kada soyayyar da kike masa ta sanya ki danne lefinsa ba fa daidai ba ne abinda ya aikata mini."
Jiki a mace ta ce." Na sani wallahi Amina, kuma bayan ke wallahi tallahi babu wanda ya kai ni jin ciwon sakin da ya yi miki, ni yadda na fahimta kamar bashi da ilimin addini mai zurfi boko ce kawai take dawainiya dashi shiyasa yake ganin kamar abinda ya aikata ba wani lefi ba ne. Abu na gaba kuma kin san shi, abinda ba na sha'awar ya kasance da ni a rayuwata wallahi kema ba na sha'awar ya faru dake, ba na yi miki sha'awar zawarci da lissafin aure don ma Allah Ya takaita gidan alhji Muntari ba ki haihu ba, wannan dalilin ya sanya nake ta dannarki ki yi hakuri ki zauna kowace mace tana da kalubale."

Na ce." Anti Yagana kada ki ce na ki jin maganarki wallahi na fahimci abinda kike gudu, amma dai don girman Allah wannan karon ki kyale ni da mutumin nan kada ki shiga ciki ki ja bakinki ki yi shiru kawai ki zuba mini ido."
"To wane shiri za ki yi akansa kin san dai shi namiji ne ke kuma mace tunda kuma ya ce ya mayar dake bafa yadda za ki yi dole ha'kuri ne naki."
Na sani anti Yagana ba shirin da zan yi akansa amma ba zan koma ba kamar yadda yake tsammani wallahi sai ya tako kafarsa garin nan."
Ta gyada kanta tanà d'an murmushi ta ce." Abu ne me sau'ki ai tunda yana sonki za ki gan shi kuwa.
Ban ce mata komai ba har ta kama hanya ta fice daga dakin.

Tun cikin dare na kammala shirye shirye na don haka gari yana wayewa na fito a kintse da zummar d'aukar hanya tunda d'akin da nake yana da bandaki ban fito ba sai da na shirya tsaf tukkuna. Gabad'aya suna falon ana shirin karyawa hadda maigidan a zaune bai fita ba dama ba kasafai yake fita da wuri ba idan juma'a ce.
Fitowata ta d'auki hankalinsu gabad'aya na gyara yanayina don ba na so ta dakatar da ni daga kudirin da na yi. A tsanake na ce." Anti Yagana na shirya fa zan tafi kamar yadda muka yi magana jiya wallahi da Gwaggwo na kwana a cikin raina."
Tana kallona ta ce." To kin gayawa mijin naki ko dai ?"
Eh kawai na ce mata a takaice. Yadda ta zuba mini ido shi ya tabbatar mini da cewa ba ta yarda da amsar dana bata bata
Yusi yana gefe a zaune ya yi nairainarai da ido saura kiris ya fashe da kuka dan tun jiyan nan dana mare shi bai zo wajan da nake ba. Kallo d'aya na yi masa na kawar da kaina daga kansa domin Ina so na horar dashi akan abinda ya aikata ko don gaba ya kiyaye furta abinda ba shikkenan ba.
Cikin sigar zolaya Babansu Fadila ya ce." Madam ba gaisuwa ne ko na yi wani lefin ne kuma."
Cike da jin nauyi na ce." Yi hakuri wallahi na d'auka dana fito na gaisheka, gabad'aya hankalina ne baya jikina."
Ya ce." Amma dai kya bari ki karya tukkuna sai ki tafi, da za ki bari ma akwai motar da zata tashi karfe goma sha daya na safe sai na kira direban yanzu."
Na ce." Anya kuwa zan bari ai ka barshi kawai zan iya shatar motar ma gabad'aya babu damuwa.
Cikin dai zolayar dai da ya saba da  sigar wasa ya ce." Au na manta Hajiya ce fa uwargidan a wurin Yallabai."
Murmushi kawai na yi na dubu anti Yagana tana tambayata yaushe zan dawo.'
Na ce." Nan da sati guda in sha Allahu zan dai kira ki idan zan taho din."
Ba ta ce komai ba ta fara tsiyaya kunun gyadar cikin wani madaidaicin fulas tana fad'in." Ki tafi dashi ko a mota sai ki kurba kina dai sauka ki kira ni."
Na ce." To shikkenan in sha Allahu......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma na #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*62*
Ganin halin da ya shiga ya sanya mini muguwar fargaba domin kuwa tunda nake dashi ban ta'ba ganinshi a cikin yanayi na rud'u da tashin hankali ba. Tabbas lokacin rasuwar baby Nana ya shiga damuwa sosai amma sai nake ganin wannan lamarin ya fi d'imauta shi fiye da wancan din. Jikina babu kuzari ko na gamin gafara na kama hanya domin fita daga d'akin saboda ban san wacesa irin fitina zamana zai haifar ba. Fargabata da tsananin damuwata kada ya fitar da maganar domin kuwa ya fi ni gaskiya da hujja mai karfi dalili ni tun farko na d'auri kaina da ban gaya masa ina da ciki ba. Idan kuwa zan kafa hujja da cewar ai na zubar da shine domin gudun haihuwar mai sikila ba kowa ne zai fahimce ni ba, da yawa ma wasu za su ga ai don ina da yaran ne ya sanya ni yun'kurin zubar da ciki ba tare da damuwata ba. Amma fa muddin an zauna an dubi lamarin ta fuskar adalci za a fahimci abinda nake nufi. Wannan kadai itace hujjata ko da kuwa maganar ta fasu na tabbatar da cewa ya fi ni hujja mai karfi domin masu k'adaita Allah da tauhidi ai za su ga gangancina domin kuwa tun fil'azal ai haka iyaye da kakanni suke yin auransu su haihu lafiya ba tare da wata rikitarwa irin ta yahudu da nasara ba.
Kai tsaye d'akina na wuce na kwanta don ba zan iya zaman falon ba dalili kwata-kwata bana cikin hayyacina ga jikina babu k'wari don har yanzu jirin bai gama sakina ba.
Anti Yagana ta shigo d'akin ta same ni a kudindine a cikin bargo lokacin ma kuka nake yi amma mara sauti sai na yi saurin rintse idona ina goge hawaye a fakaice bata fahimci komai ba tunda daga bakin kofa ta tsaya tana tambayata ko jikin ne na ce mata a a Ina hutawa ne sai ta juya ta zata fita tana fad'in bari ta kawo mini abinci na ci sai nasha magunguña.
Da kyar na iya cin loma biyar shi ma sai da ta matsanta mini tukkuna na ci sai da ta tabbatar da nasha maganin kan ka'ida tukkuna ta fita daga d'akin.
Sai bayan ishi'i su Hajja suka tafi bayan sun shigo sun yi mini sallama tare da fad'a mini cewa za su sake dawowa domin sake duba ni cikin satin da za mu shiga.
Ina daga kwance muka yi sallama cikin kulawa yadda suka nuna damuwarsu a kaina hakan ya faranta mini sosai sai dai can kasan zuciyata ina jin fargaba kad'an idan har suka samu labarin abinda na yi shin da wace fuska za su dube ni.
Tunda na fito daga dakinsa ba mu sake haduwa ba sai da garin Allah ya waye anti Yagana ta matsa mini lallai sai na rage kwanciya na fito falo na zauna

kan kujera hakan zai k'arfafa mini gwiwa domin idan ina yawan kwanciya kasala da ciwon jiki ba za su barni ba.
Saboda haka ina yin wanka na shirya na fito falon na same su suna kallo har da Baba Tabawa na nemi kujera na zauna hankali na saman ina tunanin ko ya sauko ko wane hali yake ciki.
Yusura ta kawo mini abinda suka yi na karin kummalo na kasa cin komai saboda bakina har yanzu babu d'aki. Baba Tabawa ta d'umama mini ragowar towon jiya bashi dai da yawa tunda Hajja ta tafi da wani amma ya isheni kuma ni kaina na yi mamakin yadda na ci sosai a lokacin na ji karfin jikina ya k'aru... Cikin wani yanayi na tambayi anti Yagana maigidan ya sauko tunda tun safe suna falon ta ce mini ya sauko har sun gaisa ya fita amma bai jima ba ya sake hawa saman bai kara saukowa ba kuma.
A gogon da yake falon na duba sha daya da rabi domin kada ta fahimci akwai 'baraka ya sanya na tashi ina fad'in bari na hau mu gaisa. Kai tsaye na nufi benen da zullumi mai yawa a kirjina.
Kofar d'akin kawai na tura ta bude bai murza mukkuli ba, Yana zaune a gefan gado ya shirya sosai cikin milk din shadda tazarce da aiki mai kyau a gaban rigar hularsa tana ajiye a gefe amma as'usul gilashinsa na ka'ida yana idonsa. Magana yake yi a waya a lokacin da na shiga d'akin na samu wuri gefansa na zauna amma gabad'aya na gagara kallonsa saboda tsananin yadda nake cikin damuwa.
Jin yana ambaton sunan Maryam ya sanya ni shiga tunani daga bisani Kuma na gane da Hajiya Maryam suke yin magana matar abokinsa da ya rasu kwanaki. Sun jima suna tattauna abinda ya danganci mamacin yanayin maganganunsu ya tabbatar mini da cewa suna tattauna yadda za a raba abinda ya bari tunda mahaifiyarsa ta na raye kuma yana da 'yan uwa.  Dole Mamansa ta gaje shi koda kuwa 'yan uwansa ba su gaje shi ba dalili akwai maza biyu a cikin yaranshi.
Bayan sun yi sallama ya dube ni babu yabo babu fallasa amma bai ce komai ba sai ya cigaba da latsa wayarsa yasa a kunnansa ina dai zaune Ina jin shi Hauwa ya kira a wayar cikin kulawa na ji suna magana don ba na jin abinda take cewa tunda kamar ya yi kasa da murya ne don shi ma idan ta fad'i magana sai ya sake tambayarta abinda ta ce saboda maganarta can kasa take fita. Sai na juyar da kaina gefe ganin kamar ba ya so na ji maganar da suke yi  na ji yana gaya mata daga nan din kai tsaye bauchin zai taho zuwa yamma ta tsammaci zuwansa tunda tafiyar mota zai yi.
Jikina ya d'an yi sanyi Jin yadda yake lalla'bata da rarrashi har da kalamai irin na tausayawa da sadaukarwa. Sai na tsargu da jin abinda yake yi wanda na tabbatar da cewa wanzuwata a wurin ya kawo hakan.  Na ji haushi sosai amma sai na danne domin kuwa a yanzu fushi ba nawa ba ne dalilin abinda na tabbatar da cewa ni ce mafi rinyen lefi dole a wannan ga'bar ko ban fito na gaya masa na aikata ba na nemi hanyar shiri da kuma ko'karin kwantar da matsalar don gudun fasuwar maganar.
Ya ajiye wayar a kusa dashi bayan sun kammala ya d'auki agogonshi dake saman drowar yana daurawa bai ce mini komai ba. Na daure na ce." Ina kwana Baba?"

Hankalinsa na kan abinda yake yi ya amsa da "lafiya ya gajiya." Sai na yi shiru ina dan satar kallonshi a fakaice. Sukairaju ya dan buga kofar kafin ya bashi umarnin shigowa ya turo a hankali cikin ladabi ya tsaya daga can nesa yana fad'in." Sir ka kammala ne?"
Ya mike tsaye da hularsa a hannunsa yana gyarawa ya ce." E, na kammala zo ka d'auki wad'annan." Ya fad'a yana nuna masa Loptop dinsa dake ajiye da 'yar jakarshi."
Da sauri ya yi abinda aka sanya shi ya bude kofar ya fita daga d'akin. Yana ko'karin sanya hular a saman kan sa ya ce." Ni zan tafi Amina, Amma kafin nan zan je Bauchi wurin Hauwa domin dubata ina fatan ba ki da matsala ko?''
Na mike tsaye da rashin karsashi na ce." Ba ni da matsala Baba amma ina so mu yi magana dangane da abin nan da ya furu na ga kamar ba ka yarda da kaddara ba don Allah kada ka tafi da 'kullacina a cikin ranka."
Ya dube ni sosai wanda tun shigowata d'akin bai yi mini irinsa ba.
"Kin aikata hasashen Dr Iliyasu ko ba ki aikata ba, wannan amsar kawai nake so na ji daga gare ki."
Shiru na yi ina kallonsa shi ma yana kallona ido cikin ido. Mun d'an jima a haka kafin daga bisani na janye nawa idon daga cikin nasa zuciyata na dan harbawa ko alama ban hangi sasaauci a cikin idanuwansa ba.
"Shirunki da yanayin yadda alamun rashin gaskiya suka bayyana a tattare dake ya bayyana mini ce wa." Dr Iliyas ba karya ya yi miki ba saboda haka ni kawai sai dai na ce na barki da Allah."
Daga haka sai ya kama hanyar fita daga d'akin. Da saurin gaske na cimmasa idona cike da hawaye masu radad'i na furta." Maganar bari da Allah ba adalci ba ne, ka yi duk hukuncin da kake ganin za ka yi mini tunda ka'ki kar'bar kaddara, amma kwata kwata ka daina had'ani da Allah

"Shi kadai ne zai yi mini maganinki tunda ai kin gagara Amina kin nunawa duniya cewa baki da na gaba dake kin fi 'karfin kowa ciki har da mahaifinki ni dai muddin ina da hakki akanki to fa ba zan daina cewa Allah Ya saka mini ba."
Ya sanya hannu zai bude kofar domin fita na sake tare hanyar a karo na biyu cikin jarumta na ce." Ubangiji ba mutum ba ne kamar kowa kuma akan yi masa lefi a tuba ya yafe duk sharri da bala'in da kake nema dashi da izinin Allah ba zai same ni ba domin kuwa wanda ya hallice ni ya fi ni sanin menene a zuciyata Ina ce dai idan na gaya maka gaskiya shikkenan ai ikon hukunci ko azabtarwa ko d'aukar rai duka ba a hannunka suke ba. Na yi kuskure tabbas a lokacin da na tabbatar da cikin a jikina na yi kokarin fitar dashi kamar yadda Dr Iliyas din ya gaya maka. Dana fahimci bai zube ba sai na ha'kura kawai na barwa Allah kuma na ro'ke shi gafara a sa'in da na kuskure masa kuma ina da tabbacin ya gafarta mini, abinda zan iya gaya maka kenan domin a duniyar nan babu wanda baya kuskure Ina me baka ha'kuri hakan ba zata sake faruwa ba."
Ya jima yana kallona da yanayi na mamaki da al'ajabi ni kuwa ban ji komai ba domin kuwa na lura rufe maganar da nake yi bashi da wani amfani gwara

kawai na sanar da shi gaskiyar lamari tunda ya fi ni sanin hujjata ta yin hakan.
"Hakan ba zata sake faruwa ba." Wannan maganar ya fad'a kafin a gaggauce ya bud'e kofar d'akin ya fice da saurin gaske.
Na jima ina nazarin maganar da ya furta sai na shiga zullumi da tunanin domin ya yi ta ne a d'ukunkune karshen dai hukunci shine saki a shirye nake da kar'bar gakan daga wajensa.

Da yamma muna zaune a falo anti Yagana suka yi waya da Babanmu nan take sanar dashi kwana biyu ni ce ban ji dadi ba shine dalilin da ya sanya ba mu sake zuwa ba tun ranar da aka sallameshi daga asibiti. Na ce mata ta gaya masa na ji sau'ki don zai iya tashin hankalinsa jin ba ni da lafiya
Duk da ta gaya masa haka kuwa washe garin ranar sai da suka zo duba ni tare da Baba Sule sun jima a gidan muna tattauna sha'anin Hadiza domin kuwa kowa ya riga ya mik'a wuya don a zaman kutu na farko da aka yi ba a hangi sasaauci a tare da alkalin ba. Yanzu tana can gidan kaso kafin shari'ar ta kammalu a yanke mata hukunci. Bayan sun tafi da kad'an sai ga Gwaggo Hamusu ya kawota to ita tare muka yini har dare sai bayan Isha'i, tukkuna ya taso daga shago ya zo ya d'auketa a babur ya kai ta gida.
Sai da na warware sosai sannan na gayawa Sahura abinda ya faru da ni amma ban gaya mata cewa ni ce sila ba.  Ta jajanta mini sosai tana fad'in Allah bai yi rayayyu ba ne itama haka tasha wannan wahalar lokacin da nata tagwayen suka zube ta ce mini za ta zo ta duba ni ranar da babu aiki.

****
To tafiya ta mik'a sosai don yau sati uku kenan da abinda ya faru amma tsakanina da maigidan muguwar gaba ce ta 'kullu. A zahiri shi ya d'auki lamarin da zafi na sani kowaye aka yi wa haka ba zai ji dad'i ba amma ya kamata ace ya yi hakuri ya kar'bi tubana tunda na gane abinda na yi ba daidai ba ne. Na kira shi ya kai sau bakwai tun bayan tafiyarsa na tura text amma daga karshe ma sai ya sanya ni a black list idan na kira duka layinkansa busy. Ban damu ba da farko saboda a ganina duk fushin da zai yi na dan wani lokaci ne zai ha'kura ya sauko ya kar'bi tubana ni kuma na kiyaye a gabana. Na dai ji dad'i sosai da ya rufe maganar bai gayawa kowa ba dama kuma kusan haka halinshi yake yana da zurfin ciki mussaman akan mas'ala irin wannan.

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Duk da damuwar da ta fara yi mini 'kawanya ban yarda anti Yagana ta fahimci wani abu ba har dai ta tattara ta tafi bayan an yi zaman kotu daya da ita inda ake tsammanin zama na gaba za a yanke hukunci na karshe.
Bayan tafiyar anti Yagana Ummansu Hadiza ta zo mini a ki'dime tana kuka sosai duk ta figale ta lalace wai na taimaka na daukarwa Hadiza lauya domin

kuwa a cikin lauyoyin gwamnati an rasa wanda zai kar'bi case din ganin haka ya sanya kowa yake tunanin zama na gaba  Hadiza za ta san matsayinta.
Na rasa yadda zan yi da ita domin dai Ina ji Ina gani ba zan daurewa karya gindi ba. Hadiza ta fad'a da bakinta tana da hannu dumu-dumu shedu sun shaida to me zai sanya haka kawai na d'aukar mata lauya saboda son zuciya. Kuka take yi sosai tana gaya mini halin da Alhajiji yake ciki shi ma yana can hannun 'yansanda a jos suna azabtar dashi  mahafinsa da 'yan uwansa da suka uba daya sun ce babu ruwansu ga Hadiza ma za a yanke mata d'aurin rai da rai."
Na rasa kalmar da zan yi amfani da ita wurin rarrashinta domin kuwa Allah ne kadai ya san irin rad'adin da take ji a cikin zuciyarta.
Ban yaudareta da zumar zan yi mata abinda take buk'ata ba. Na dai rarrasheta da tausasan kalamai na kuma jadadda mata ce wa ta mikawa Allah lamarin sannan kuma ta tsananta da addu'a Ubangiji zai kawo mata d'auki.
Da zata tafi na bata dubu talatin na ce kuma Ayuba ya kaita har gida don abincin ma dana sanya a kawo mata bata ci ba sai juye mata na yi a leda ta tafi dashi.

***
Yau wata biyu kenan da tafiyarsa wanda ya yi daidai da abinda ya faru da farko da na ce ba zan kara kiran shi ba amma yau tunda garin Allah ya waye na tashi da wata irin kewa da sha'awa. Na zauna ina tunanin abinda ya janyo mini shiga yanayin tunda na farko ni ina gujewa sha da cin duk abinda zai daga mini hankalina babu namiji a kusa da ni. Amma yau din nan na wayi gari da tsananin kewa kuma tasa da son jin wani abu daga gare shi.
Duka na bi layinkansa ina busy har yanzu bai cire ni ba, na duba shi a ta whasap na ga ya sauka tun kwanaki uku da suka wuce.
Sallama na yi masa cikakkiya da addu'ar Allah Ya sa ya amsa mini a duk lokacin da ya bud'e ya ga sa'kona.
Na kasance koyaushe cikin duba shi ta whasap din tsayin kwanaki tara da tura sa'kona bai hau ba sai yau. Na ga alamun ya duba sallamata amma kuma bai ce komai ba ya ma sauka.
Sai na sake tura masa wata sallamar again ina ta addu'a Allah Ya sa ya magantu.
Bai duba ba sai da gari ya waye tukkuna nan ma dai bai amsa mini ba.
A takaice dai sai da na yi masa sallama sama da biyar ya bud'e ya ga ni amma ko d'aya bai amsa ba.
Raina ya 'baci ainun. wannan mummunan dabi'arsa tasa ta gaba tana mugun b'ata mini rai. Kuma na fahimci  yana da rike abu a zuciyarsa ba kasafai ake bashi ha'kuri ya ha'kura a lokaci daya ba.
Sai kawai na share shi  gabad'aya ni ma na fita daga sabgarsa duk kuwa da cewa tunani da kewarsa na d'an damuna amma dai Ina yun'kurin dannewa domin tsira da sauran mutuncin da ya rage mini......✍️
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*64*
Wannan kukan da nake yi ya zama me mini dole ne na yi shi domin yinsa kad'ai zai sanya mini jin sasaauci a zuciyata. Amma kuma tilas ne fa na yi wani abu akan wannan lamarin namu domin sanin matsayin da nake a zamantakewarmu.
Haka dai na yi hakuri na danni zuciyata da 'karfin addu'ar da na dimanta na d'an ji sa'ida a cikin raina, amma dai duk da haka idan lamarin ya fado mini a raina na kan shiga wani yanayi mara dad'i.
Na cigaba da kasancewa cikin tunani da nazarin yadda zan b'ullowa alm'arin. Kai tsaye shawarar da na yanke a raina itace zan nufi maiduguri gidan Baban Saude na san shi kad'ai ne zai dube ni ya kuma fahimci halin da nake ciki. Nasan kuma zai ri'ke ni kamar 'yar cikinsa a wannan karon ba zan ce zan yi zaman kaina ba balle a canza mini manufa a iya tunanin da na yi shine gidan Baban Sauden dai shine marufar asirina babu wanda zai zarge ni da wata niyya na ke ko'karin kashe auran. Ba zan gayawa anti Yagana komai ba itama sai dai kawai ta ji labarin ina garin. Kuma na tabbatar da cewa babu wanda zai zo ya ce zai tursasa ni akan abinda ba na so muddin na ci sa'a Baban Saude ya kar'bi kukana ina da ya'kinin zai iya yin gaba da gaba da Alhaji Tajon sai dai duk abinda zai faru ya faru.
Ina ta shirye-shiryen tafiya ban gayawa kowa ba shawarar da na yanke shine Yusura za ta koma hannun mamanta itama baba Tabawa zan sallameta da alheri mai yawa, masu gadin gidan da Ayuba dama ba ni na ajiyesu ba. Ina shakkar Babanmu ya samu labari abinda na tabbatar da cewa ranshi zai b'aci matu'ka da gaske. Hakan ba zai sanya ni na janye ba domin kuwa Babanmu zuciyarsa ba irin ta kowa ba ce ba zai iya ta'buka komai ba ko da kuwa an zube magana an tabbatar da cewa ni ma ina da gaskiya ta wani gefan ana cutar da ni.
Sati uku da d'aurin auransa inda wa'adin rantsuwar da na yi akan rashin zuwansa ya kusa cika saura sati daya kenan wattanin bakwai da barinsa garin.
Hajiya Saratu ta kira ni a waya tana gaya mini Hajja babu lafiya har sun je da ita Egypt sun yi sati daya sun dawo gida amma jikin da sau'ki yanzu. Na ce mata wallahi ban sani ba da tun wuri na zo na dubata. Mamaki ta dinga yi wai saboda na ce mata ban sani ba, ganin kamar tana so ta fahimci wani abu ya sanya na yi mata sallama tare da bata tabbacin in sha Allahu Ayuba zai kawo ni gobe na dubata.
Kwana biyu a tsakani Ayuba ya kai ni gidan Hajja na dubata jiki da sauki alhamdulillahi ta warware don tana zaune ma ana ta hira, ni ma na saki

jikina sosai domin ko da wasa ban nuna akwai wata matsala ba. Cikin hirar da muke yi ne na d'an fahimci wani abu ashe maigidan ya zo garin har ya yi kwanaki ya koma a cikin tsakankanin wannan lokacin bayan sun dawo daga Egypt .
Shiru na yi da suna maganarsa ban iya cewa komai ba domin kuwa ni ban san ma ya zo har ya tafi ba, amma can 'kasan zuciyata abin ya tsorata ni sosai ya kuma sanya mini shakku anya maganar Sahura bata tabbata ba kuwa ko dai da gaske ne matar nan Maryam da ya aura tana asiri tunda mijinta har ya mutu da ita kadai ya rayu.

Wannan littafin na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba

Tunanina ne ya katse a lokacin da na ji Hajja tana maganar ai ya je can bauchi wurin Hauwa wadda take daf da haihuwa ko yau ko gobe domin kuwa sun yi waya da inna Uwani ta ce mata kwanansa biyu a can kafin ya tafi.
Jikina ya 'kara yin sanyi kwarai da aniya tabbas mutumin nan ya sake ni furta mini ne kawai bai yi ba saboda mugunta ya jingine ni a gefe d'aya.
Ina jin su suna ta hirar abinda ya shafe su, idan ta had'o da ni na sanya musu baki amma kuma zuciyata cike take da mamaki lamarin to sunce ya zo ya kwana amma me yasa basu fahimci cewar ba ma tare ba. Idan har ya zo din ai a gidana ya kamata ya sauka  bayan ya duba mahaifiyartasa. Wani sashe na zuciyata ya ce mini tunda ki ka ga basu fahimci komai ba to wata'kila bai gaya musu wata matsala ba kuma ai yana da gidajen a garin da guesthouse bai zama lallai ya kwana a gidanki ba, idan ya yi musu sallama da zummar tafiya wurinki ai ba zasu fahimci komai ba."
Wannan hasashen na zuciyata shi ya zauna daram a k'wa'kwalwata. Wato abinda ya yi kenan har ya yi kwanakinsa anan din ya tafi bauci wurin matarsa ba su gane komai ba. Ganin haka ya sanya ni ma na cigaba da nuna fara'a da annashuwata ban yarda yanayina yayi sauyarwar da za su gane akwai matsala ba. Da suna hirar Hajiya Maryam amaryarsa ni ma na sanya bakina Ina biye musu domin kuwa ga dukkanin alamu ta samu karbuwa a wurin Hajja tana sonta don sai fad'in alherinta take yi. Tabbas matar ta san takan zama tare da duniyanci domin kuwa koda bata asiri zai wahala duk wanda ya kusanceta ya ga laifinta domin ta iya mu'amula da kyautatawa. Gashi dai 'kiri-'kiri sun mayar da ni sauna ita da shi sun kar'be mini yarona duk tsananin sha'kuwar da take tsakanina da Yusi idan mun had'u sai na zama bak'uwa a wurinsa. Yadda ma za a yi ya dawo hannuna a yanzu shine abinda ya fi daga mini hankali da sanya mini fargaba domin kuwa yadda ya d'aukaki mutumin  nan kamar shine wanda ya haife shi. Haka zalika ma ta b'angaransa shi Yallabai din ya sanya yaron a cikin ransa wanda yake nuna kamar ya ma fi ni iko da shi.

Yini na yi sai yamma na yi shirin tafiya Allah sarki Hajja ta had'a mini Turaruka masu tsada da k'amshi na jiki da kuma na wuta dana tsinke.

Zuciyata ta tsinke k'warai da gaske domin kuwa na tabbatar da cewa ta ji labarin bada'kalar da take faruwa hankalinta zai tashi wanda hakan ka iya yin barazana da lafiyarta. Na kuma gane dalilin da ya sanya shi kansa yake 'boyewa saboda tabbatuwar kwanciyar hankalinta tunda ni din ta gaban goshinta ce in banda yanzu da magauta suka yi yawa amma zahiri Hajja tana sona k'warai, kuma tana son zamana da d'anta.

(Ga masu buk'atar a tallata musu hajarsu ina yi cikin farashi mai sau'ki a yi mini mgn 08089965176)

Ranar da na shirya tafiyar  laraba ce wadda na tabbatar da cewa Sahura tana wajan aiki ba za ta yi yun'kurin zuwa ta dakusar da ni ba  sai dai ta dawo gida ta samu Yusura da Baba Tabawa. Akwati biyu na yi ta kayana na hada komai dana tabbatar da cewa zan buk'ata. Muka yi waya da Hamusu na gaya masa zan je maiduguri ya cigaba da kula da komai wanda dama hakan aikinsa ne. Bai kawo komai a cikin ransa ba muka yi sallama. Na umarci Ayuba ya fito da mota kai tsaye  gidan Sahura muka nufa aka yi sa'a Idiris yana gidan bai fita kasuwa ba tukkuna tunda lokacin da muka fito daga gida tara da rabi na safe. Tun a mota muka yi sallama da Baba Tabawa na bata dubu hamsin na ce ta ri'ke a hannunta amma tunda na sanya mata lambata a sabuwar wayar dana saya mata duk lokacin da take da wata matsala ta kira ni ta gaya mini zan tura mata da kudi. Ta kama hanya ta tafi gidanta kad'an da gidan Sahura. Ita Yusra sai da muka shiga gidan tare sauran yaran duk suna makaranta a gurguje na tsaya muka gaisa da maigidan yana tambayata lafiya dai na ce masa kalau zan je maiduguri shine dalili. Na mik'awa Yusra dubu biyar ta kar'ba jikinta duk a sa'bule na kama hanyar fita a gurguje ina cewa dashi ya gayawa Sahura zan kira ta a waya idan na isa.
Tashar kasuwar kwari na ce da Ayuba ya kaini. Ya tsaya yana jayayya wai na fadi inda nake so na je zai kaini tunda akwai wadataccen mai a motar kuma aikinsa ne hakan idan oga ya ji labarin hakan zai yi sanadin rushewar hanyar abincinsa.
ganin yana yi mini taurin kai ya sanya na  rufe shi da fad'a sosai na ce ya sauke ni muddin ba zai yi abinda na ce dashi ba. Ganin yadda raina ya b'aci ya sanya shi jan motar bai sake magana ba kuma kai tsaye inda na umarceshi ya nufa da ni.
Muna isa na bude motar na fito. Shi ma ya fito da sauri ya d'auko mini akwatinana. Mota guda na d'auka domin ba zan iya jira ba. Ban ma tsaya yin sallama da Ayuban ba na ce da direban ya shigo mu tafi. Ina kallonsa ya koma motar jikinsa a sanyaye kuma har direba da nake cikin motarsa ya ja muka tafi shi bai bar tashar ba.
Tun a mota na kira Baban Saude dama kwanaki uku da suka wuce mun yi waya dashi na fara gaya masa halin da ake ciki ya ce mini maganar ba ta waya ba ce sai na zo tukkuna sai mu tattauna. Na sanar dashi cewa gani nan akan hanya ya yi mini fatan alheri da sauka lafiya.
Sai daf da magriba muka isa maiduguri na sake d'aukar mota har kofar gidan Baban Saude yana tsaye a kofar gida fuskarsa kadaran kadahan har na fito

daga motar direban yana sauke akwatinana.  Ya k'araso wajen da muke tare da kiran yaronshi dake wasa a can tsallake ya rugo da gudu wajan ya umarce shi ya d'auki akwatin kayana ya shiga dashi gida.
Yaron ya d'auki babbar akwatin da sauri ya nufi gida da ita. Shi kuma ya sunkuya zai d'auki k'aramar. Da sauri na ri'ke tare da cewa." Haba Baba bari zan shiga da ita."
Ba tare da ya ce mini komai ya saki akwatin na d'auka muka jera muna tafiya yana fad'in. " Kin ci sa'a yau kwanana uku da dawowa kuma na kan d'auki sati ko kwana goma ban koma ba, Amina wannan lamarin naki ai abun a zauna ne domin kuwa ba karamin abu ba ne. Ni namiji ne amma ba na goyon bayan azzaluman maza."
Murmushi na yi tare da furta." Wallahi Baban Saude tura ce ta kai bango ha'kurina ya kare akan lamarin nan, domin kuwa duk yadda na so ganin na zauna abin ya ci tura kamar yadda na gaya maka yau wata bakwai kenan rabona dashi kuma duk ya rufe hanyar da zata had'ani dashi to kaga zamana ai bashi da amfani yana da kyau ace a neme shi domin ya sanar da manyana abinda ya yanke akaina.....

Wannan badakala ta Amina da Tajo. Allah Ya yayyafawa abin ruwan sanyi.......
✍️
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*65*
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Don kuskure kin yi, amma hakan ai ba zai sanya a d'auki wannan mummunan matakin akanki ba ai idan ba yana so ya jefa ki a wata masifar ba me zai sanya ya k'aurace miki na irin wannan watannin wannan ba daidai ba ne an shiga hurumin addinin Allah tabbas
 akan hakan dole mu neme shi domin mu ji me yake nufi. Sai maganar zargi da rashin daidaituwar jini gabad'aya ma auran naku ai a baibai yake babu dacewa ai ta wani gefan kema kina da hujja Amina, na kuma ji dad'in da ki ke neme ni domin sanya ni a cikin lamarinki zan yi kokarin ganin na samar miki da farinciki in sha Allahu rabbi."

 Gidan Baban Saude mai yalwa ne kuma daidai gwargwado yana da rufin asirinsa don har yanzu da rayuwa ta yi tsadar nan shinkafa 'yar gwamnati ake ci a gidansa. Taliya 'yar hausa kuwa sai dai idan sun yi  sha'awa yadda yake jingine musu buhun shinkafa ta gwamnati haka yake ajiye masu kwalin taliya da makaroni na waje da sauran kayan masarufi, shi din  mutum ne mai

wadata iyali matsalar kawai fa'da da tsautsauran ra'ayin takura iyali domin kuwa kafin a fita unguwa a gidan Baban Saude akan jima sai dai idan da 'kwa'kkwaran dalili.
Matansa biyu kowacce da yaranta da d'akunansu ciki da rumfa ne manya. Akwai shaguna biyu daga waje wanda ciki matasan yaransa maza suke kwana cikin gidan kuma bayan d'akunan iyalinsa akwai falle falle biyu masu grima sai kicin da bandaki biyu na fitsari da kuma na ba haya sai wadataccen tsakargida mai yalwa don har da bishiya a tsakiyar tsakar gidan.
Sayyada ce kawai take zawarci dama lokacin da anti Yagana ta je mini take gaya mini ai an sasanta anti Saude da anti Zainab sun koma d'akin mazajensu amma kafin hakan sai da aka sha daru domin shi cewa ya yi raba auran zai yi. Sai da Dada ta yi masa jan ido tukkuna ya janye matakin da ya d'auka domin idonsa ya rufe baya duba kowa dama ai hausawa suka ce kowa nasa ya sani, shi yana duban 'ya'yansa yayin da mazajen suma suke duba wahalar da nasu yaran za su shiga muddin aka raba su da iyayensu. Anti Saude itace babba don ta girmi ma anti Yagana amma da kad'an kuma yaranta bakwai, ita kuwa anti Zainab haihuwarta biyar daya ya rasu hud'u a raye amma duk da haka ya ce shi sai an sakar masa yaransa kuma ya tubure lallai babu d'an da zai d'auka ya yi wa wahala kowanne yaro ya koma gidan ubansa. Gabad'aya ma sai sanya dokar kada a kuskura a sake barin yaran su shigo masa gida.
Wannan matakin da ya d'auka shi ya gigita anti Zainab tunda ita nata akwai k'ananu a ciki kuma ita kadaice bata da kishiya mijin nata ya d'auki yaran ya kaiwa yayarsa ita kuma kullum ficewa take yi kasuwa ta baza hajarta. Anti Saude ce mai kishiya kuma yaranta sun girma sannan kuma duk maza ne. Anti Zainab kuwa da mata a ciki.
Tashin hankalinta ta yi sosai babu shiri a 'boye ta je gidan Dada ta fashe mata da kuka tana gaya mata yadda aka yi tare da neman alfarma kada ta gayawa Baban nasu itace ta gaya mata.
Wannan shine dalilin da ya sanya Dada ta bud'e masa wuta akan lallai ya nemi mazajensu ya zauna dasu ya ja musu kunne amma banda maganar rabuwa a duba yaran domin kuwa hukuncin da ya yanke ba shine mafita ba tunda dole ai watarana za su sake yin aure kuma mazan ba 'kwan'kwasasu ake yi a ji ba.
Ita kuwa Sayyada da yake itace auta a mata kuma sunan Dada ne da ita dama tun kafin a yi mata aure 'yar lele ce tunda ya fahimci mugun miji take aure mara ciyarwa da kula da lafiya sai kawai ya maka shi a kotu akan ya sakar masa 'yarsa ya kuma fadi ko nawa ya kashe a lokacin da zai aureta zai biya shi tunda shi ya nemi sakin dama kuma haihuwarsu d'aya saboda farincikin Sayyadar ya bar yaron nata a hannunta domin kuwa kuka ta dira a gidan bayan alkali ya raba auran ta ce ita ba zata bada yaro ba. To da yake dama 'yar lelensa ce sai ya kyaleta ya ce mata amma muddin ubansa ya zo nemansa za a bashi abinsa.

D'aki guda ya sanya a ka gyara mini tsaf har da katifa da sabon mashinfid'i da labuleye masu kyau d'akin yana ta k'amshin turaran wuta irin na tsinke.

Mama uwarginshi da kanta ta shigo ta kawo mini abinci a jere a tire na silba muka sake gaisawa bayan wadda muka yi tunda kafin na shiga masaukina sai da na shiga duka d'akunansu muka gaisa. Ta dinga tambayata mutanan gidanmu da yaran na ce mata duk kowa lafiya lau.
Sai da nayi wanka tukkuna na d'an warware na ji 'kwarin jikina na zauna a nutse na ci abinci na 'koshi na fita da tiran ina sake yi musu godiya na koma d'akin na zauna tare da fito da wayata daga cikin jaka domin tun a cikin mota ban sake dubata ba. A mace take ban san dalilin da ya kasheta ba.
Minti biyar da kunna wayar kiran anti Yagana ya shigo. Cike da fad'uwar gaba da fargaba na d'aga  nasa a kunnena cikin wani irin yanayi na yi sallama bata amsa mini ba na ji tana ce wa." Ya aka yi ki ka kashe wayarki Amina tun wajan la'asar nake kiranki sai a ce mini a kashe take."
A hankali na ce." Bacci na yini ina yi kuma tunda na sanyata a caji ban sake waiwayenta ba sai yanzu ina fatan kuna lafiya ina Fadila."
A takaice ta furta." Lafiya lau, mijinki ne ya kira ni yake tambayata wai kin zo gidana na ce a a wani abun ne ya faru a tsakaninku ne?"
Cike da takaici na ce." Babu abinda ya faru anti Yagana don girman Allah idan ya sake kiranki kada ki daga wayarsa."
"Akan wane dalili zai kira ni na'ki dagawa Amina, ki gaya mini menene yake faruwa domin yanayin da ya kira ni a d'azu ya tabbatar mini da cewa akwai abinda kuke b'oyewa ke da shi."

"Saki na ya yi."
Na tsinci kaina da gaya mata hakan.
Cikin rud'u da tashin hankali ta furta." Saki akan wane dalili, kina ina yanzu domin ya tabbatar mini da cewa tun safe ki ka fito daga gidanki direbanki Ayuba ne ya kira shi a waya ya gaya masa shine ni kuma ya kira ni yake tambayata."
Cikin dauriya na ce." Anti Yagana abinda nake so dake a wannan ga'bar da muke ci da mutumin nan don girman Allah ki cire kanki idan zai kira ki sau dubu ya tambayeki abinda ya shafe ni ki ce masa ba ki da k'arfi akan lamarin ya nemi manyana su yi magana, don rainin wayo ne kadai zai sanya ya dinga nemanki ai ya san wad'anda suka bashi aurena tunda ina da uba kuma yana raye ke menene na ki a ciki."

Ta shiru na dan wani lokaci kafin ta ce." Eh kwarai kuwa ba ni da ruwa a ciki Amina shishshigi ne ma ya sanya nake kutsa kaina a sha'aninki, ba ni da hannu tabbas ni ba kowa ba ce."
Jin yadda ta juya maganar ya sanya a sanyaye na furta." Anti Yagana ki yi hakuri don Allah kada ki juya mini manufa ni da ba haka nake nufi ba."

Ta ce." To na ji, ko zan iya sanin abinda ya faru, sannan kuma ki gaya yanzu kina ina domin hankalina ya kwanta Amina sha'aninki yana nema ya fi karfina, don girman Allah ki fahimci kin girma fa kina dai kallon abinda ya samu Hadiza ko, mune manya a gidanmu ba mu da namiji babba dole mu zamu tallafi 'kannanmu da suke tasowa don Allah ki yi hakuri ki jure kamar

yadda kowace mace take ha'kuri a d'akin mijinta ki zauna wannan ya zama mutuwa ce zata raba tsakaninku ki yi mana wannan alfarmar." Ta kare maganar cikin rawar murya.
Ina kuka na ce." Anti Yagana ya zan yi ne da rayuwata gabad'aya duniyar ta yi mini zafi a yanzu bana jin dad'inta. Duk yadda zan yi na yi kokarin ganin na zauna d'akina amma abin ya gagara, Allah Ya had'a ni da wani irin (Ba'aboren namiji) sunan littafin Binta Umar Abbale ku nema ku karanta ya yi mutukar dadi.
Tana kuka irin mai tafe da tsananin damuwa da takaici ta cigaba da cewa." Abubuwan da suka faru tsakanina da shi suna da yawa anti Yagana na gaji da b'oye miki na kuma gaji da zama da mutumin nan so nake  yi kawai ya sauwake mini na huta idan ba so yake yi zuciyata ta buga ba."

A sanyaye ta ce." Dalili dame bakincikinsa zai kashe ki Amina, ai taura biyu bata taunuwa a lokaci daya babu yadda za a yi ace a shari'ar ma'aurata an saurari b'angare daya ni ba zan yarda da maganarki ba har sai ya zo tukkuna an zauna an zube magana sai a fahimci wanene mafi rijayen lefi."
Cikin kukan na ce." Anti Yagana ke fa macace ya kamata a ce kin dubi halin da nake ciki,  ki fahimce ni wallahi ina da matsala ba wai da gangan nake so auran nan ya mutu ba ina da hujja mai karfi."

Wannan littafin na kudi ne yar uwa kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba. Ina 'yan kasuwar da suke so a tallata musu hajarsu ina yi akan farashi mai sau'ki.

"Hujjarki ai bata wuce kina gudun haihuwar yara masu cutar sikila ba dalili kuwa shine rashin had'uwar jini. Wannan ce kad'ai hujjarki wadda na sani Amina, sai kuma kishin da yake damunki tunda na ji labarin an ce ya sake yin wani auran, in bayan hakan ban san wani abu da ki ka taka ba. Sannan kuma ai kai tsaye ban ce miki baki da gaskiya ba, cewa na yi a bari a ji ta bakinsa tukkuna kafin a yanke hukunci wannan shine adalci, ai duk yadda zan so shi bayanki ne, matsalar namiji kuwa muddin ki ka ce ba za ki iya d'aukarta ba to Amina kina tare da damuwa domin kuwa kusan gabad'ayansu haka suke.
Na ce." Wallahi anti Yagana ban da Babansu Fadila a ciki, ai ya yadda ki ka kasa fahimtar damuwata tuntuni na tabbatar da cewa ba ki kai ajin da nake ba dangane da karatun namiji, maza uku fa na aura kuma kowa da halinshi wallahi ban ta'ba shan wahala a hannun Yaya Aminu da Alhaji Muntari irin wadda nake sha a hannun mutumin nan ba. Ku ne kawai  kuke yi mini kallo hutu da jin dadin amma ni kadai nasan irin takaicin da nake 'kunsa."

Murmushi ta yi har sai da na ji sautinsa ta furta." Ha'kuri dai kawai na fi ki shiyasa ki ke ganin kamar ba ni da wata matsala da mijina. Amma kai tsaye ba zan musanta miki ba domin kuwa mai-d'aki shi yasan inda yake yi masa yoyo abinda nake so dake anan shine ki gaya mini kina ina yanzu hankalina zai fi kwanciya."
Kai tsaye na ce." Ina nan gidan Baban Saude yanzu haka."

Cike da zullumi ta furta." Gidan Baban Saude fa ki ka ce Amina?"

"Kina da hankali kuwa Amina, shin ko kin manta halin Baban Saude da d'aukar jidali akan abu 'kalilan zai mayar dashi babba. Mai yasa ba ki yi shawara da ni ba tukkuna kafin ki yanke wannan hukuncin sanin kanki ne Alhaji Tajudden ya yi nisan da wani mahalu'ki zai kai ya ta'ba mutuncinsa ko da babu dukiya kuwa to akwai dattijanka da girma da mutuncin da zai wuce a ce kina yawon kai shi a k'ara, kuma duk ki tsallake 'yan uwan Babanmu saboda raini ki taho wurin Baban Saude saboda dama kin tabbatar da cewa shi din ba mutum ne mai nisan tunani da tsinkaye akan lamari ba. Yanzu me ki ke tunanin zai faru idan har ya kashe miki aure wallahil-azim ba ni babu ke Amina." Ta kàrasa maganar cikin tsantsar tashin hankali da damuwa......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*66*
Sosai kaina ya d'aure da jin maganarta. Wai yau anti Yagana itace take kiran Baban Saude da mutum mara tsinkaye saboda wani na daban, ta manta cewa Baban Saude ciki daya suka zauna da Mamanmu. uwa daya uba daya ba wasa ba ne, kuma wallahi duk tsayayyar da yake yi akan gaskiyarsa yake mutane ne suke ganinsa masifafe mafadaci wanda ba shi da mutunci, kuma wallahi fahimtarsa ne kawai da ba a yi ba. Shi baban Saude irin mutanan nan ne masu tsage gaskiya duk d'acinta. Babu ruwansa a ko'ina yakan fad'i ra'ayinsa kuma ko ta mutu ko ta yi rai, tuntuni na fahimci anti Yagana bata cikin jerin mutanansa domin ko da na gaya mata zan sanar dashi halin da nake ciki da farko dakusar da ni ta dinga yi tana ganin idan har ya ji abinda yake faruwa zai iya dagula lamarin ya sake rinca'bewa. Daga haka kuma auran ya mutu abinda take ji wa tsoro kenan, wanda ni kuma a wannan ga'bar da nake ciki ban'ki auran ya mace ba kowa ya huta. Domin kuwa ban ga alfanu da cigaba a tattare da zama da wannan mutumin ba.
Ba na shakka ko fargabar had'uwarsu da Alhaji Tajon ai mutunci da sanin ciwon kai ya fi komai a rayuwar wanda yasan kansa. Baban Saude ba makwadaici ba ne ballantana yana ganin gaskiya ya take da gangan. Ai da take cewa na gaya Babanmu ko 'yan uwansa babu abinda zai iya yi balle kuma baba Sule da gabad'aya bai yi ba. Makwadaici ne na gaske babu wata ho'bbasa da zai iya yi domin 'kwatar mini 'yancina. Babanmu zan yi shedarsa ba shi da kwadayi yana da gudun duniya da kuma dogwaro da kansa. Idan an bashi zai kar'ba da godiyar Allah amma ba zai roka ba duk shaharar arzikin mutum, ya iya ri'ke talaucinsa, kuma da zai d'auki mataki tuntuni ai

da ya d'auka, babu wani abu da za su iya yi mini sai dai su danne ni kamar dai yadda ita anti Yaganar take dannata.
Ni gabad'aya ma na rasa gane inda ta dosa wallahi da ban san halinta ba da sai nace itama kudinsa take kwad'ayi. To na san halinta da kawar da kai da kawaici akan abin mutum sam bata da wannan zulamar. Abin mamaki wai yau anti Yagana ce take cewa idan na rabu da wani namiji ita da ni har abada. Sai kawai na ji wasu zafafan hawaye sun k'wace mini suka fara kasa tsere a kumatuna. A hankali na ajiye wayar na silale na kwanta saman ledar dake tsakar d'akin Ina wani irin kuka mai ciwo lallai mutumin nan ya yi wa rayuwata illa ta kowane 'bangare, kokari yake yi da gaske sai ya shiga tsakanina da 'yar uwata jini daya bayan fin karfin da ya yi mini wurin raba ni da yarona duk kuwa da tsananin shakuwar da take tsakaninmu kamar ya sanya almakashi ya datse yanzu ganin Yusi ya yi mini tsananin wahala balle na ji muryarsa, wannan wace irin masifa ce!

Wajejan sha biyu na dare na tashi na je na d'auro alwala nafila na yi raka biyu cikin sujjadar karshe na fashe da kuka tare da kai wa Allah kukana akan ya za'ba mini abinda ya fi alheri a rayuwata muddin rabuwata da Alhaji Tajon akwai alheri to Ubangiji Ya gaggauta kawo k'arshen lamarin. Idan kuma zamana dashi bai kare ba ina ro'konsa ya daidaitamu cikin ruwan sanyi ba tare da an kai ruwa rana ba rayuka sun 'baci ta dalilin hakan.
Na kwanta bacci da jin sasaauci a zuciyata domun kuwa ina kammala addu'ar na ji nutsuwa ta shigeni tare da tawakkali da kar'bar duk irin abinda Allah Ya zartar a kaina.
Da safe bayan na yi wanka Sayyada ta kawo mini kayan karin kummalo d'akin da nake ta zauna muna d'an ta'ba hira jefe-jefi kafin ta fita daga d'akin domin ba ni damar karyawa a nutse.
Gama karin kummalona ke da wuya Babansu Fadila ya zo wato mijin anti Yagana lokacin Baban Saude ya fita zuwa babban gida wajan Dada domin su gaisa.
A soro na same shi a tsaye da shirin fita wajan sana'arsa muka gaisa kafin ya fara yi mini maganar da ta kawo shi domin jiya duk wayar da muka yi da anti Yagana a gabansa ne kuma shi ma a jiyan da magriba ya ga gilmawarta a tasharsu sai yake hasashen anya ni din ce domin bai gama tabbatarwa ba sai da ya dawo gida tukkuna ya tabbatar da cewa ni din ya gani bayan saukata a garin.
Nasiha da ban ha'kuri tare da kawo misalai irin na matan magabata ya dinga yi mini har yana cewa ko don yadda 'yar uwata take shiga damuwa matsananciya akan matsalata yana da kyau na jure na yi hakuri na samar mata da nutsuwa domin kuwa jiya raba dare ta yi akan dadduma gaban Allah tana addu'a da hawaye akan lamarin. Wannan dalilin ya sanya shi ma ya kasa rintsawa har garin Allah ya waye kuma ya kudire a ransa cewa zai zo ya same ni akan abinda yake faruwa.

Hakika sun ba ni tausayi sosai ita dashi kuma sun isa su ce mini na yi ko na bari ba tare da na yi musu jayayya ba. Amma a wannan karon Ina ganin ba

zan iya bin umarinsu ba domin kuwa duk abun nan da ake yi shi wanda ake yi dominsa bai yi wata magana ba, bai zo ba tun bayan kiran da ya yi wa anti Yagana jiya ban sake ji daga gare ta ba.
Hakan na gaya masa na ce ya bari tukkuna ya magantu ai yanzu dama a hannunsa take idan yana da ra'ayin cigaba da zama da ni zai zo ya nemi sulhu idan kuma bashi da ra'ayi to zai aiko mini da shedar da zata nuna mini lallai ya gama zama dani, Ina ganin kamar haka ya dace a yi.
Sai ya nuna ai ba haka ya dace a yi ba tunda ai anti Yagana ta gaya masa har yanzu na'ki na fadi abinda ya yi mini kuma ba shine ya ce da ni na tafi gida ba yaji na yi na bar d'akina don haka kuwa tunda ba shine ya ce na tafi ba ai babu lallai a ce sai ya nemi inda nake domin ya ji dalilina.
Na jima ina nazarin maganar kafin daga bisani na yanke shawarar gaya masa abinda yake faruwa tunda ai shi din ba bare ba ne, sannan kuma maganace da za a zauna a zube ta shi ma makusancina ne tunda yana auran sha'ki'kiyata.

Duk bada'kalar da take faruwa na zayyana masa da irin ni ma abinda na aikata da tuban da na yi sannan kuma na tabbatar masa da cewa na gane kuskurena na kuma nemi afuwa da gafarar Allah da kuma neman sulhu da shi domin mu yafi juna amma hakan bai yi masa ba har sai da ya d'auki hukuncin kaurace mini na tsayin wattanin tare da shigowa garin ba tare da ta nemi inda nake ba .

Sosai al'amarin ya dake shi ya jima yana nazari kafin daga bisani ya dube ni da alamun tausayi da sasaauci ya ce." Ni ai duk ba ta gaya mini haka ba Amina ta dai ce mini kawai tana zargin ke ce ba ki son auran ki ke so ki kasheshi amma ba ta gaya mini dalili ba
A hankali na furta." Ai ba ta sani ba don ban gaya mata ba har yanzu saboda na san halinta da sanya abu a ranta kuma bai zama lallai ta fahimce ni ba, in banda kai da Baban Saude babu wanda na gayawa sai ko Sahura 'kawar nan tawa.
Ya ce." Lamarin na ku ne da rikitarwa Amina, kina da kuskure shi ma yana da nasa kuskuren ai dama ba za a d'auki lefi a daurawa mutum d'aya ba. Kuma gaskiya abinda ya fi tsaya mini a raina dangane da lamarin nan yawan zargin da ki ka ce mutumin nan yana yi miki babban abu ne a ganina wannan ba soyayya ba ce domin kuwa zargi yana daya daga cikin manyan dalilan da suke saurin lalata ala'ka ta auratayya. Ba zai yiwu a ce don ya aureki a matsayin bazawara kuma 'yar kasuwa ya dinga zarginki ba sam ba shi da hujja ko a wurin Allah domin kuwa bai ta'ba kama ki da wani mummunan abu ba. Sai maganar tsayin wattanin da ya d'auka ba tare da ya neme ki ba, wannan normal ne Amina akwai matan matafiya da suke shekara da biyu uku ba tare da mazajensu ba kuma aurensu bai lalace ba sai dai kin san shi addini kogi ne domin ni kaina na ji wasu malaman suna cewa idan namiji ya k'auracewa mace na tsayin wata uku hud'u biyar har zuwa shekara to aure ya haramta a tare dasu amma fa sai in dai suna kwana tare a gida daya ya aikata hakan. Idan sun yi nesa da juna kamar dai matafiyi wannan ba lefi ba

ne haka daga shekara daya zuwa biyu aure yana nan. To anan za mu iya cewa auranku yana nan tunda baya garin da a ce kuna gida daya ne kuna kwana a daki daya ya k'aurace miki tabbas akwai alamun a tambayi malamai domin sanin menene gaskiyar lamari. Wannan shine iyakacin fahimtata.

littafin nan na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Sannan ke ma zan gaya miki gaskiya abinda ki ka yi bai kyautu ba domin kuwa kin shiga hurumin Ubangiji dalili kuwa ai shine mai rayawa da kashewa kuma bai zama lallai don kin haifi d'aya da lalura ba ki ce duka yaran da za ki haifa haka suke ba. A lokacin da ki ka lura da samuwar cikin sai ki bar shi kawai ki ro'ki Allah ya ba ki masu albarka kuma masu lafiya. Abu na biyu kuma kin ga mutumin nan bashi da yara shi zai so ko masu lalurar ne wannan kadai ya isa ya sanya shi ya k'ullaceki kuma ya ga duhunki domin kuwa ai zai ga kamar kina yi masa b'akinciki ne saboda wata hujja taki wadda bata da tushe balle makama, sannan da yawan mutane ba zu fahimceki ba domin kuwa za a ga ai ke ko dan kina da yaran ne ya sanya ki ka zubar masa da nasa cikin. Lefi ne babba ko wurin Allah Amina amma kuma na ji dad'i da ki ka gane gaskiya kuma ki ka nemi gafara a wurin Allah lallai Ubangiji mai afuwa ne kuma mai yafiya ne, sannan kuma shi ma Yallabai din yana da kyau ya yafe miki ya d'auki 'kaddara domin ta riga fata bai kamaci ya d'auki wannan matakin ba domin a ganina da tun farko kun kashe matsalarku a cikin gida hakan zai fi alheri ba tare da kowa ya sani ba domin kuwa irin wannan lamari baya buk'atar a ce a zauna ayi ta nanata shi saboda kowa da irin fahimtarsa wasu suna gyarawa ne wasu kuma na 'batawa."

Tun a 'karshen maganarsa na fahimci gugar zana yake yi mini akan Baban Saude wata'kila kafin zuwansa nan din anti Yagana ta gaya masa halinsa shiyasa yake yin shagu'be shi ma yana nuna rashin dacewar kawo maganar wajan Baban Saude ni kuma gabad'aya duka sun kasa gane dalilina. Ban kawo 'karar Alhaji Tajo wurin Baban Saude da zummar ya wulakantashi ba, ni kaina nasan wargi ma wuri shi ka samu. Baban Saude idan yana yi wa wasu ya zauna lafiya ina ganin kwarjini gami da haiba irin na Tajudden ya wuce a ce ya yi masa tijara mai muni. Ina dai da tabbacin cewa za su yi musayar yawu irin na fahimta domin a samu matsaya akan abinda yake faruwa.....✍

*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*

*07084653262*

*08089965176*

*V-VIP AREWA PEN*

*67*

Wajejen sha biyu na rana Sahura ta kira ni a waya a nutse na d'auka muka gaisa amma babu cikakkiyar walwala a tare da ita fara da cewa." Yanzu sis ashe dai sai da ki ka sanya kafa ki ka shure shawarata ko? jiya na dawo daga aiki na tarar da Yusra a gida da yamma Baba Tabawa ta shigo tana gaya mini kin yi tafiya zuwa maiduguri gaskiya ba zan boye miki ba ban ji dad'in abinda ki ka yi ba domin kuwa yanzu nan muka gama waya da anti Yagana tana tambayata wai ko nasan wani abu da yake faruwa game dake."
Ta nisa kafin ta cigaba da cewa." Na ce mata kin gaya mini amma kin ce sirri ne, shine ta ce to na bar shi ba sai na gaya mata ba tunda amana na kar'ba a wurinki. Sai kawai ta kashe wayar a sanyaye Ni kuma gaskiya na ji rashin dadin hakan mai yasa ki ka boye mata abinda yake faruwa da rayuwarki Amina bai kamata ace har sai ta fito duniya tana neman dalili ba."
Murmushi na yi mara armashi na ce." Sahura hakan da na yi shine kwanciyar hankalina da kuma samun nutsuwata don Allah kada ki ka ga lefina kada ki 'kullace ni, addu'a kawai nake so ki taya ni da ita, sannan maganar anti Yagana kuma ni na fi kowa sanin halinta kwata-kwata ba ta kar'bar uzurina in dai akan mutumin nan ne to bata ta'ba fahimtata kamar yadda ke ma ba kya gane nufina. Wannan dalilin ya sanya ban gaya mata ba domin lefinsa za ta take da k'afarta ta rufe gabad'aya ta d'auka ta d'ora a kaina, to shiyasa ko da na yanke shawara ban nufe ta ba kai tsaye na yi tafiyata a gidan Baban Saude."

Ajiyar zuciya ta sauke a hankali ta ce." To ke yanzu me ki ka yanke a zuciyarki rabuwar ki ke ganin itace mafita a gare ki ko kuwa, tunda kina ganin kin fi karfin ki d'auki shawarata Amina to ni menene sai kin gaya mini ba'kar magana a fakaice. Kowa rai ya yi dad'i ai barin mai shine. Ni dai tun tasowarmu ban ta'ba saninki da wannan mugun taurin kan ba, sai da Allah ya rufa miki asiri ki ka ji kina kama 'yan-canji tukkuna ki ke ganin karanki ya kai tsaikon da za ki iya cin mutuncin kowa. Tuntuni na sha gaya miki aure ibada ne shiyasa iyayenmu koyaushe suke jaddada mana mu kyautata ha'kuri domin kuwa shine kaso mafi rinjaye a zamantakewa irin ta aure. Na gani da idona na ji labari a bakin da ba zai kirkiri 'karya ba oga yana sonki irin son da yake da wahalar samu. Yana ta tataki yana yi miki duk abinda ki ke so. Kin zubar masa da ciki saboda tsabar son zuciya kin tafi yawon kai shi k'ara gari ya gari har maiduguri kamar wannan mutumin Amina anya kina da hankali kuwa..... Ba tara kàrasa ba na katseta da saurin gaske domin kuwa zuciyata ba zata iya jure hatsaniyar da take yi mini ba. Sahura bata ta'ba ba ni haushi ba irin yau. A fusace na furta." Na kai shi k'arar Sahura shi din wanene Annabi ne ko kuma walliyin Allah da har ake gudun 'bata masa rai. Ina ruwana da dukiyarsa mutum ne fa kamar ni mai tarin zunubai mai kashi da fitsari, mai yasa zan tsaya jin tsoro da shakka a kansa tunda yana tsuguno a masai kamar yadda nake yi. Ai da yana da bambamci da sauran hallita ne sai na saurara masa. Na gane dake da anti Yagana so kuke na zauna 'bakincikinsa ya kasheni to akan wane dalili. Shi kadai ne namiji a duniya da har zan jira yana b'ata mini rai, bai fi karfin na kai shi 'kara ba wallahi tunda ni dai abin hannunsa bai bude mini ido ba. Yarana suna

buk'atata to ban ga dalilin da zai sanya na zauna wata hallita tana kuntuka mini ba." Na kare magana ina nishi saboda tsananin b'acin ran ganin yadda mutumin nan yake nema ya shiga tsakanina da makusantana.

Itama da tsananin b'acin rai ta furta." Ni ina nema a wurinsa kuma ina ci da sha a karkashinsa na gode miki da ba'kaken maganganu da kuma gori, ki cigaba da yin fito na fito da umarnin Allah da kafarki za ki taka siradi tunda mutumin nan kin zalince shi kin kuma sa'bawa Ubangijin da ya hallicceki."
Jin muryarta tana rawa ya sanya na sassauto a hankali na ce.'" Sahura don girman Allah kada ki juya mini bayana, ki tuna irin gwagwarmayar da muka yi a baya, kada ki yadda mutumin nan ya raba zumuncin da yake tsakaninmu don Allah ki fahimceni wallahi yana zalintata. Na yi lefi na bada ha'kuri, na tuba ga Allah to a yafe mini mana menene za a dinga yi mini gashin 'kuma a fakaice idan dama mutum bai taki wani abin ba.

Ta yi shiru na dan wani lokaci kafin ta ce." To shikkenan na ji, yanzu me ki ka yanke akan abinda ki ka yi?"

"Ban yanke komai ba Sahura sai abinda Allah Ya zaba mini, idan har rabuwar itace alheri ina farinciki da hakan, idan kuma akwai sauran zama a tsakaninmu to gaskiya ba zan koma ba lallai sai ya fahimci cewa abin fa da yake aikatawa kuskure ne, sai ya dauki matakin gyara da alkawari tare da sharad'in hakan ba zata sake faruwa ba.

Murmushi ta yi irin na takaici kafin ta ce." Amina wani lokacin ina mamakin tsaurin idonki wallahi to wai Baban Sauden ki ka wakilita da ya kira Yallabai din ya titsiye shi akan kuskuran da mafi rinye ke ce mai shi. Idan fa an bi ta 'barawo to a bi ta mabi sawu na gaya miki tun ranar da na zo gidanki wallahi ke ce mai lefi mai yasa za ki zubar masa da ciki saboda wani banzan dalili da bashi da tushe. Son zuciya ne fa wannan tsagwaronsa ki ka nuna masa a zahiri saboda ke ai kina da yaran shi kuwa fa. Ki bari ki haihu mana ki ga abinda za ki haifa da lafiya ko babu kawai sai ki yankewa Allah hukunci, ba zan gaji da gaya miki ba, baki da gaskiya."
Cike da tsantsar takaicin kasa fahimtata da ta yi har yanzu
Na ce." Ban kyauta ba din Sahura duk abinda za ku yi ku yi din, haba na gaji da magana daya wai ana aure dole ne ko kuma tilas aka ce sai na zauna da mutumin nan da za ku bi ku tsangwameni. uwata ce ke da za ki kira ni a waya kina gaya mini maganar da ranki ya so, ko kuma ke ce ki ke zaune da mutumin nan ne, kwata-kwata kun kasa fahimatata, na yi kuskure na nemi afuwar Allah amma gabad'aya kuna juya mini magana saboda kawai wani dalili naku. Ina kara jadadda muku shi ai ba sahabi ba kuma ba Annabi ba ne da ba za a 'bata masa rai ba. Ko annabawan Allah suna kuskure balle wani bawa kuma Allah Ya yafe musu saboda haka a yanzu daga ke har anti Yaganar ba na buk'atar ku fahimce ni, duk abinda za ku yi akan lamarin kun jima ba ku yi ba." Ina gama maganata na kashe wayar raina a mafisar b'ace. Tunda muke da Sahura ba mu ta'ba musayar yawu mai zafi irin wannan ba.

Haba na gaji da jan magana d'aya muddin ba za su gane hujjata ba to sai mu yi ta tafiya a haka ba zan sake yarda wata ta kira ni a waya ta 'bata mini rai ba.

Wannan littafin na kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Da takaicin abinda yà faru tsakanina da Sahura na yini duk yadda na kai ga ko'karin ganin sun fahimceni ita da anti Yagana abin ya gagara har sai da sa'bani ya gifta a tsakanimu, to kuwa ta yaya za a yi kuwa na manta da mutumin nan tunda ta dalilinsa anti Yagana take furta maganar da ban ta'ba tsammanin fitowarta daga bakinta ba, wai za ta rabu da ni har abada saboda shi yau ga Sahura tana gaggaya mini ba'kaken maganganu. Ban ta'ba nadamar saninsa ba a rayuwata sai a wannan lokacin.
Da daddare muna zaune a babban tsakar gidan gabad'aya har da maigidan Baban Saude an shimfida masa dadduma mu kuma muna zaune a 'katuwar tabarma ana ta hira cikin nisha'di cikin raina ina ta mamakin hakan wato duk wanda zai k'alubalanci Baban Saude akan wani lamari tabbas ba zai zauna dashi ba ne, sannan kuma bai gama karantar hali da d'abi'arsa ba.

Dada da Anti Yagana suka yi sallama a lokaci daya suka shigo gidan. Ganinsu a tare ya sanyayar mini da jiki domin kuwa na tabbatar da cewa anti Yagana ce ta je ta gaya mata abinda yake faruwa.
Suka zauna akan tabarma ana gaisawa Baban Saude yana cewa da Dada ba ta gaya masa za ta zo ba a d'azu da safe da ya je can gidanta domin su gaisa.
Sai ta kuwa ta kada baki ta ce." Ni ma dole ce ta sanya ni zuwa ai domin kuwa abinda ka boye mini shi Yagana ta je ta gaya mini shine na ce bari na zo da k'afafuna gidan naka na ji dalilin da ya sanya ka b'oye matar mutane a gidanka, idan har za ka yi iko da yaranka Haruna wannan dai baka da k'arfi a kanta kuma babu yawuna a cikin yun'kurin da ka ke ko'karin aikatawa."
Cikin nutsuwa ya ce." Wato Yagana ce ta je ta taso ki da daddaran nan kenan, kin kyauta Yagana na ce kin kyauta." Ya fad'a yana kallonta da b'acin rai a tare dashi ita kuma sai ta yi kasa da kanta tana cike da damuwa ta furta." Baban Saude don Allah ka yi hakuri wallahi ba nufi na ba ne na bata maka rai, amma ni nasan Amina bata da wata hujja gabad'aya ma majority lefin nata ne tunda d'azu Babansu Fadila da ya zo ta gaya masa duk abinda ya faru wanda ni ta rufe mini saboda ta san ba zan goyi da bayanta ba."
Ya ce." Shiyasa ki ka je ki ka gayawa Dada kenan saboda ni ban isa na yi hukunci ba, ko kuma ni zan goyi da bayan k'arya ko?"
Ta yi shiru tana girgiza kanta alamun ba haka ba ne.
Ya gyada kansa da takaici ya dubi Dada tare da ce wa." Duk abinda Yagana ta je ta gaya miki akan Amina kada ki amince da cewa ita kadai ce take da laifi domin shi ma mijin nata da akwai tasa matsalar, kuma yana da kyau ace yarinyar nan an dubi matsalarta an kuma d'auki matakin gyara. Ba ni da

burin kashe mata aure sai dai idan har hakan ya zama dole, sannan kuma ni babu ruwana da wanda take aure dukiya nasaba ko wata d'aukaka ta mutum. Ni namiji ne amma ba na goyon bayan mazajen da suke zalintar matansu ta kowane 'bangare. Wannan dalilin ne ya sanya da yawa mutane suke yi mini kallon mafad'aci saboda tsage gaskiya. Dada babu yadda za a yi yarinya ta kira ni a waya tana kuka akan wata matsalar da ta dameta na ce babu ruwana a ciki dalili wata hujja dan ban zo a b'angaran mahafinta ba to ban ga dalilin da zai sanya na ja baya akan lamarinta ba, idan na yi hakan kuwa tabbas ban dubi zumunci ba, kuma ban yi wa 'yar uwata kara ba. Ba dalili ba ne a ce wai dangin babanta ne lallai suke da hakkin kare mata mutunci ba, to idan kuma suka gaza fa, ma'ana suka kasa ta'buka wani abu akan lamarinta shikkenan sai ta zauna a hannun wanda bai san daraja da mutuncinta ba......✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*68*
Wajan ya yi tsit kowa ya yi shiru yana sauraransa. Ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Tun kafin ta zo nan ta gaya mini halin da take ciki a waya da kuma ta zo ta sake jadadda mini duk abinda ya shiga tsakaninta dashi da abinda ta aikata masa da matakin da ya d'auka akanta. Dan Kuskure ta yi kuskure kuma ban goyi da bayan ta sake aikata hakan ba ko bayan raina na gargad'eta domin hakan fasadi ne mai girma. Ta kar'bi lefinta ta yi nadama ta tuba ga Allah kuma ta nemi gafara to me zai sanya ba za a yafe mata ba. Wannan sune kadai matsaltsalun Amina, kuma na ja kunanta kwarai da gaske akan ta gyara ta kiyaye a gaba. Ba wai ina goyon bayanta ba ne a yanzu ta ce ba ta da ra'ayin zama dashi cikinmu babu wanda ya isa ya yi mata dole domin kuwa ita ba yarinya ba ce ta san abinda yake mata ciwo sannan kuma tana da hujja ko a gaban alkali za ta fad'a masa dalilinta na son rabuwa da auransu saboda matsalar rashin daidaituwar jini da za a samar da yara masu ingantaciyar lafiya. Abu ne ya zo a zamanance ba mu ce za mu yi wa Allah wayo ba, amma zahiri lalurar nan akwaita dalilin da ya sanya ma kenan aka fara d'aukar matakin kare kai daga riskar abinda zai faru bayan an yi aure. Amma fa wannan bayanin nawa baya na nufin cewa ina goyuwa da bayan yahudawa ba ne a a ko daya domin kuwa ni kaina a lokacin da na auri iyalina babu gwaji na jini kuma ga yara na nan duka mun haifa lafiyarsu lau babu wani mai lalura daga ciki. Saboda haka Dada ki fahimce ni anan

wannan ga'bar kada a tilastawa yarinyar nan a ce dole sai ta cigaba da zama da bawan Allan nan alhalin bai san girma da mutuncin ba."
Dada jikinta ya yi sanyi sosai duk karsashin da ta shigo dashi gidan babu shi a tare da ita a sanyaye ta ce." To yanzu na ji abinda kace Haruna, amma ya za ka yi ka hadu da mijin nata kasan dai shi ba yaro ba ne idan ma ka girme shi ba yawa kuma sannan ba irin mazajen yaranka ba ne da kasa ba yi musu tsawa da gindaya musu sharad'ai."
Dariya ya yi irin ta manya a tsanake ya furta." Ai na girme shi Dada, kuma yana auran 'yata duk kudi da wani abinda yake ji dashi ya zame masa dole ya ajiye a gefe guda kafin ya tunkaro inda nake muddin yana so mu daidaita. Ni wani kudinsa ba zai rud'a ni ba, ke kan ki kin san da wannan Dada."
Wani irin sanyi na ji ya sauka a zuciyata ta yi fes lallai Baban Saude ya shirya kare mini mutuncina.
Ya dubi anti Yagana babu fara'a ya ce." An ce yana kiranki a waya to na gargad'eki duk lokacin da ya sake kiranki akan lamarin ki ce masa ya nemi inda nake kuma ki sanar dashi daf nake da komawa wurin neman abincina domin ina sa ran a satin nan da za mu shiga asabar ko lahadi zan tafi muddin kuwa ya bari na tafi bai neme ni ba to sai na dawo kuma"

Cike da damuwa da kar'bar umarni ta ce." To shikkenan in sha Allahu don d'azu ma mun yi waya da shi har yana sake jadadda mini cewa shi bai saketa ba bayan wanda ya yi mata a baya shi kad'ai ne ya san wànda ya yi har yanzu akwai sauran igiyoyin auransa biyu a kanta."
Gyada kansa ya yi yana gyara zamansa ya ce." wannan kuma abinda ya shafe shi ne, ki yi dai yi kokarin bin umarina idan ya tuntubeki akan matsalarsa ki ce masa ya nemi inda nake domin kuwa matarsa tana hannuna."
Ta ce." To in sha Allahu rabbi."
Kwanan farinciki na yi a ranar saboda irin tsayuwar da Baban Saude ya yi akaina na ji dad'i kwarai da aniya kuma na yi masa addu'ar samun lada a wurin Allah.

***

To kwana uku a tsakani zuwansu Anti Yagana da safe ina bacci Sayyada ta shigo tana tashina wai Baban Saude yana kirana. Da zullumi na tashi na fita na wanke bakina sannan na nufi d'akinsa da yake can gefe da tsakargidan na yi sallama a nutse na shiga yana zaune da tukunyar shayi da mangal a gabansa ya gama dafa shayin yana tsiyayawa a kofi. Na sake gaisheshi duk da cewar d'azu kafin na kwanta mun gaisa. Ya amsa yana d'an motsa shayin da cokali kafin ya dube ni a tsanake ya ce." Jiya Yagana ta kira ni a waya ta gaya mini mijinki ya bu'kaci da a bashi lambata shine take neman izini na ce ta bashi babu komai to shine yanzu nan ya kira ni a waya yake gaya mini cewa yana nan tafe gobe juma'a komai dare zai shigo akan maganarku shin ya kike gani. Ni ba zan yi miki dole ba fa Amina domin kuwa ba kowane yake zaune da mutumin nan ba sai ke, idan har kin ga da 'kwara da cutarwa a ciki to ni don na ce masa ya sawwa'ke miki ba abu ne mai wahala ba a wajena.

Idan kuma kin ga kina so ki cigaba da zama dashi sai a ja masa kunne tare da gargadin wannan ya zama na farko ya kuma zama na 'karshe idan har bai daina ba a gaba sai a d'auki matakin rabuwa ko yana so ko baya so tunda akwai al'kalai, shari'a kuma tana kan kowa da mai kud'i da kuma mai mulki.
Shiru na yi ina nazarin maganarsa. Babu shakka Baban Saude ya cika jarumin namiji domin kuwa abinda ya yi a yanzu ba kowanne zai iya yi ba dalili shi wanda za a titsiye din mutum ne wanda Allah Ya wadatashi da farcen susa ya kuma rataya masa taguwar arziki.

Na ce." Baban Saude idan har na rabu da auran mutumin nan duniya za ta zage ni. Sannan anti Yagana za ta 'kullece ni tunda har yanzu ta kasa fahimta. Ga 'kawata aminiyata Sahura mun samu matsala da ita duk ta dalilin haka. Zan cigaba da hakurin zama dashi muddin an nuna masa cewa abinda ya ke yi mini ba daidai ba ne, idan har ya gyara kuskuransa ni kuma na yi maka al'kawarin in sha Allahu rabbi zan yi kokari wurin ganin mun zauna lafiya, kuma zan kiyaye abinda zai sake kawo sa'bani a tsakaninmu kamar yadda ka yi mini nasiha."

Gudun aure littafin kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya jima yana kallona kafin ya gyada kansa a nutse ya furta." To Allah Ya yi miki albarka, ya kuma kare faruwar hakan anan gaba, sannan kuma ki yi amfani da duk shawarwarin dana d'ora ki akai, kina kallon yadda iyalina suka karanci halina tsaf to sai mu jima wata matsala bata gifta mana ba suna bina a yadda nake so, ni kuma ba na zalintarsu daidai gwargwado ina sauke hakkin kowacce. Ina so ki yi koyi dasu a dan zaman da ki ka yi tare dasu, ki d'auki darasi na zamantakewa tunda kina da abokanan zama to sai ku zama 'yan uwan juna, ku taimaka juna, ku ha'de kan yaranku waje daya, kada ku yarda wata 'baraka ta raba zumuncin yaranku a gaba za ku yi alfahari da haka. Sannan kuma kada ki kara samun ciki ki zubar wannan maganar na nanata miki ki ri'keta da kyau domin ba ke ki ke rayawa ba, haka zalika ba ke kike kashewa ba, tunda har kin yarda za ki cigaba da zama dashi a hakan to Ina yi muku fatan alheri Ubangiji Allah Ya sa har karshen rayuwarku wata matsala ba zata sake faruwa ba."
Hawaye na ji sun ciko idona saboda tsananin mutuwar jiki. Wato ana zaton wuta a ma'kera ashe Baban Saude mutumin kirki ne na gaske ban sani ba, lallai anti Yagana da mutanan da suke masa wani irin kallo sun d'auki alhakinsa domin kuwa mutum ne nagartacce mai mayar da d'an wani nasa, irin wad'annan mutanan masu tsage gaskiya da gudun abin duniya sun yi 'karanci a wannan duniyar.

Ina komawa d'aki anti Yagana ta kira ni a waya na daga tare da jin d'an faduwar gaba domin kuwa ban san dame take tafe ba. Sama sama ta amshi gaisuwa kafin ta fara gaya mini dalilin da ya sanya ta kira ni a waya. Na ce

mata ai yanzu ma Baban Saude yake sanar da ni komai. Sai ta ja tsaki da alama har yanzu ciki take da ni don dai na yi mata nisa ne babu yadda za a yi ta zo inda nake ta huce fushinta saboda sanin halin maigidan , shiyasa haushina da take ji ya sake ninkuwa. Shiru na yi Ina sauraran duk maganganun da take yi uffan ban ce mata ba domin Ina iya yin magana ta ce na yi mata rashin kunya domin mu rabu lafiya duk abinda ta ce mini sai na ce to, ta kashe wayarta bayan ta gama gaggaya mini maganganun da ranta yake so da sunan jan kunne da gargadi akan zuwan da zai yi har tana cewa tasan ba ni da mutunci za a iya had'a baki da ni a wulakantashi da tozarci saboda yin hakan a wurin Baban Saude abu ne mai sau'ki dalilin da ya sanya ta kira ni kenan ta gaya mini sun yi waya dashi tun jiya kuma ya tabbatar mata da cewa da zummar sulhu zai zo.

Ajiyewar wayar na yi raina fes cikin zuciyata na ce da ke dashi dukkaninku ba kwa son gaskiya, ko yanzu ai na tauna tsakuwa don aya ta ji tsoro, na d'auka ai girman kai ba zai bar shi ya tako kafarsa ya zo ba, ai na ji dad'i mutuka da gaske da yadda Baban Saude yake da kafiya da dagiya akan ra'ayinsa. Duk da kwarjini da haibar da yake da ita ina da tabbacin hakan ba zai firgita Baban Saude ba dalili shi ma mutum ne mai ra'ayin rik'au kuma mai tattare da wadatar zucci.

Washe gari da safe bayan mun karya kummalo na koma na kwanta bacci mai nauyi ya d'aukeni ko kadan ba na tare da wata fargaba ko zullumin abinda zai faru idan ya zo garin shiyasa kwata-kwata ma ban sanya abin a raina ba don ni har so nake ma ya zo din naga yadda za ta kaya wannan shi zai nuna mini cewa yana sona da gaske ko kuwa duka karya ce da yaudara.
Sai wajan daya na rana na tashi rana gatse-gatse ina fitowa tsakar gidan da zummar wanke bakina da burushi na sami matan gidan suna ta aiki na yau na daban ne domin Sayyada na hanga a can cikin kicin ta dasa kujera tana ta suyar kaji. Mama tana gyara alayyahu ita kuma anti amarya tana tace zo'bon da yake kan wuta.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*69*
Ina gama wanke bakin na shiga cikinsu muna aikin tare cikin zuciyata Ina tunanin ko saboda zuwan mutumin nan ya sanya Baban Saude yin wannan hidimar. Shiru dai na yi ban tambayi komai ba har muka kammala aikin gabad'aya towon farar shinkafa tas da miyar taushe wadda ta ji gyada da

alayyahu gefe guda ga soyayyan man shanu nan da ya ji albasa. Ga soyayyun kaji nan masu yawa wanda Sayyada ta yi aikinsu.
Bayan mun gama komai tsaf na share gidan na wanke shi tas lokacin Baban Saude ya fito daga dakinsa da zummar wankan Juma'a. 'yan samarin gidan ma daya bayan daya duk suka shigo suka yi wanka suka yi shirin massalaci. Ana saukowa Baban Saude ya shigo da dadduma a kafad'arsa ya tsaya daga bakin kofar d'akin Mama lokacin muna ta aikin daura zobo a leda ya ce maza a fito da abincin nan akai wa almajiran massalaci kamar dai yadda aka saba. Salmanu shi ma yaronsa ne shi ya shigo ya rataye daddumar a kan taga kafin ya kinkimi kular towon ya fita da sauri Abahuraira shi ma ya shigo ya d'auki kular da aka zuba miyar a ciki ya fita da ita.
Da yake girkin anti Amarya ne itace ta had'a masa abincinsa a babban tire ya ce ta kai d'akin dai ta ajiye zai sake fita domin yana da ba'ko. Umarninsa ta bi ta yi yadda ya ce mata.

Muna cin abinci ina nazarin yanayin yadda Baban Saude ya tsara gidansa da rayuwarsa komai a tsanake babu harido babu hauka kawunan iyalinsa a had'e babu ba'kar gaba balle kishi mai tsanani. Sayyada ce take gaya mini ai duk ranar juma'a akan yi abinci mai kyau a kai massalaci akalla ya fi shekara goma yana wannan aikin ladan amma a cewarta na yau na daban ne domin kajin da ya sayo sun ninka wanda yake saya duk Juma'a. Jin haka ya sanya na gazgata zargina saboda zuwan Alhaji Tajo ne domin karramashi. Wannan ya kara tabbatar mini da cewa Baban Saude yana da kyawun zuciya kuma ba shi da niyyar kashe mini aure ko tozarta mutumin nan
Sai dai idan har ni na bu'kaci hakan.

Bayan la'asar hud'u da arba'in da shida Baban Saude da kansa ya fita domin zuwa airport ya taro shi. Kafin ya tafi sai da ya leko ya sanar da ni tukkuna sannan ya tafi.
To sai a lokacin ne jikina ya d'anyi sanyi na dan dinga jin fargaba amma ba sosai ba. Wanka na yi na shirya cikin doguwar riga amma ban yi wata kwalliya ba turare kawai na fesa a jikina na zauna gefen katifa da wayata a hannuna ina dubata. Tun ranar da ya d'ora hotunan d'aurin auransa ban kara ganin status d'insa ba, dama kuma ban ta'ba gani din ba, hakan sai ya k'ara tabbatar mini da cewa don na gani ne yasa tunda a lokacin ina ta neman hanyar da zamu shirya.

Koda na tuna irin wulakanci da rashin arzikin da ya dinga yi mini a lokacin sai raina ya 'baci na ja tsaki tare da gyara kwanciyata a katifar ina tunanin akan wannan tsohuwar matar ya ki'dime matar da ko wadataccen nono ba ta dashi k'aramin jiki ne da ita bata da wani tudu ta baya a tsuke take har gwara Hauwa da 'yar cikar 'kuruciya a tattare da ita. Ai na godewa Allah da ya sanya duk su biyun babu wadda za ta nuna mini kyawun jiki ta ko'ina har yanzu da komad'ata.

Ina daga cikin d'akin a kwance na ji shigowarsu ina jin muryar Baban Saude sama sama amma ban ji abinda yake cewa ba. K'amshin turaransa har d'akin da nake kwance k'amshin da hancina ya jima bai shak'a ba.
Zaune na tashi ina laluban mayafin rigar da take sanye a jikina gefe guda kuma gabana na d'an bugawa kad'an kad'an yanayin jikina ya fara sauyawa da wani lamari na daban..

Sai da na yi namijin ko'karin wajan ganin na rinjayi zuciyata don gudun kada ta kunyatani a gabansa. Ba ni da halin cire son da nake masa a zuciyata domin da damar a hannunata take ni kuma nake sarrafa zuciyata to ina ganin da ba wannan maganar ake yi ba. Ni kaina nasan Ubangijina ya jarrabe ni da kaunarsa inda Allah Ya taimakeni rauni na bai ta'ba barin na nuna masa mahaukaciyar soyayyar a fili ba, Ina ganin da ya fahimci haka wulakancin da zai yi mini sai ya fi wannan.

Kusan minti talatin da zuwansa Ina zaune a d'aki ni kadai ina ta tunanin mai yake faruwa a d'akin Baban Saude kuma ban ji ya kira ni ba, can na ji maganar Dada da sauri na tashi na fita na tsaya a bakin kofa tana d'akin Mama suna gaisawa ina tsaye a bakin kofa hannuna ri'ke da labule hankalina na bakin kofar d'akin Baban Saude takalma na gani uku a bakin kofar d'akin a zube ina tsammanin har da Babansu Fadila za a yi zaman domin na ji muryarsa a dakin. Dada ta fito daga d'akin Mama tana magana wadda ban fahimci me take cewa ba ta dube ni muka had'a ido sai ta ja tsaki kafin ta furta." Dube ta da ido a tsaye kamar an kama 'bera a massalaci, ashe abin naki duk karya ce."
Na bita da kallo ina gyara yanayina da tunanin maganarta to mai ta hanga a tare da ni da har take fad'in wannan maganar.
D'akin Baban Saude ta nufa tana cigaba da yin k'ananun maganganu wanda kad'an na tsinta daga ciki tana ce wa." Mu a lokacin mu ina muka san wani kai 'karar miji balle yin jayayya dashi da ganin daidai ake da juna, ai duk macan da tace  ba zata yarda ta zauna a kasan mijinta ba tana tare da wahala shiyasa auran yanzu ai baya karko.''
Na dinga kallonta da bugawar zuciyata to me kuma ya kawo wannan maganar idan dama ba ta shirya tsinka ni a wurinsa ba, Ina ce ai tun kafin a yi wannan zaman Baban Saude ya gaya mata abinda ya faru. Shine kuma za ta zo ta canza magana. Gabana ya cigaba da fad'uwa na koma cikin d'akin na zauna jikina duk a sanyaye hakika ban ji dadin gayyatota da aka yi ba domin kuwa za ta iya fad'in wasu maganganun da zai sake bashi kwarin gwiwa, kuma da take cewa su a da ba haka suke yi ba to yaushe zata had'a mazan da dana yanzu, ai yanzu lamarin rijalu ya lalace domin kuwa da yawa daga cikinsu basa tsoron Allah wasu ma idan baka fito ka nuna musu cewa daidai ake ba to ba za a zauna lafiya dasu ba. Da yawa akwai mazan da sun fi so idan sun ce kule a ce musu cass! a hau sama a fad'o a tare a buga a goga hakan ya fi musu dad'i, amma wallahi idan suka samu mace saliha mai bin su sau da kafa sun fi yi mata iyashege da shegantaka.

Hankalina yana kan agogon da yake kafe a bangon d'akin biyar da rabi yanzu ina lissafi lokaci a k'alla yanzu ya yi awa daya da zuwa amma ba a neme ni ba, ai na d'auka ni ma za a zauna da ni domin idan ya fad'i abinda ban yi ba na kare kaina kuma a shirye nake da na amsa lefin da na yi na bashi ha'kuri.
Har na cire tsammanin cewa za a yi zaman da ni na ji muryar Baban Saude daga cikin d'akinsa yana kwala mini kira. Na amsa da sauri tare da tashi zumbur na d'auki mayafin rigar jikina na rataya a wuyana na zura takalmi na fita.

Littafin nan na kudi ne, don girman Allah kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

A nutse na shiga d'akin tare da sallama gabad'aya suka amsa har da shi da yake zaune a gefan Baban Saude Dada da babansu Fadila kuma suna zaune a waje daya. Gefe guda kuma kwanukan da suka ci abinci ne a ajiye. Gefan Dada na zauna ina 'kara daidaita yanayin da nake ciki.
A nutse na dubi Babansu Fadila na gaida shi ya amsa da sakin fuska kamar yadda muka saba gaisuwarmu cikin mutunci.
Sai da na sake daidaita yanayina tukkuna na dubi gefan da yake zaune muka had'a ido da juna domin dama tun shigowata na lura da cewa idanuwansa suna kaina. Na ce." Barka da yamma ya hanya?"
Ya amsa babu yabo babu fallasa da "Barkanmu dai ya kike?''
Shiru na yi ban sake cewa komai ba, d'akin ya d'auki shiru na sakkoni kafin Baban Saude ya yi gyaran murya a nutse ya dube ni yana ce wa" Amina tun kafin na kira ki zuwa nan mun tattauna abinda ya had'a mu anan mijinki kafin ya fadi aibunki sai da ya gama fad'in alhenki sannan ya fad'i dalilin da ya sanya shi yi miki wannan hukuncin domin horone a gare ki. Ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Kamar yadda ki ka tuba ki ka kar'bi kuskuranki haka nan shi ma a yanzu kafin shigowarki na nuna masa illa da rashin dacewar abinda ya yi, domin kuwa ganganci ne mai girma tare da yun'kurin lalata aure kauracewa mace na tsayin wannan wattanin. Hakan ba daidai ba ne, kuma an yi wa addini tare da koyarwar Ubangiji kutse. Ni ba malami ba ne amma a iya sanina wannan abin da ya aikata kuskure ne, kuma gashi nan a zaune ya yarda kuskuran ya yi amma ya fadi hujjarsa wadda ba yi tsamarin ace an yi wannan kauracewar ba.
Annabin rahama bai hore mu da mu hora matayenmu ta hanyar kaurace musu tsayin wani dogon lokaci ba. Ya hore mu a duk lokacin da iyalinmu suka mana wani abu na kuskure. Annabi S.a.w Ya ce." Ku nesanta kanku gare su na takaitacen lokaci ko kuma ku k'aurace musu a shimfida ku buge su kadan da gefan rigar jikinku. Gashi nan a zaune ya nuna mini ya yi nadamar abinda ya aikata amma ya fadi hujjarsa ta yin haka a cewarsa idan ya kasance a kusa dake a koyaushe zai iya d'aukar matakin da rayukan kowa zai 'baci wannan shine dalilin da ya sanya ya k'aurace miki na tsayin wannan watannin ammana tare da bin sha'aninki domin sanin halin da ki ke ciki.

Ya yi shiru kafin ya sake numfasawa ya cigaba da ce wa." Kamar yadda ki ka yi mini alkawarin cewa za ki cigaba da zama dashi a haka to ina horanki da cewar wani abu makamancin abinda ki ka aikata kada ya sake faruwa idan kin samu ciki irin na haihuwa ki barwa Allah domin dukkanin hukunci yana hannunsa.
Mijinki ya tabbatar mini da ce wa shi ma har yanzu yana sha'awar cigaba da zama dake domin yana sonki wani dalili mara karfi ba zai sanya shi rabuwa dake ba ko da kuwa Allah bai kaddara masa haihuwa ba. Saboda haka Dada da maigidan Yagana za su zama shaida a tsakanin zaman nan da muka yi wanda nake da burin Allah Ya sa ba za a kara maimaitama shi ba a tsakaninku, idan matsala ta fuskantoku za ku yi maganinta a junanku tunda dukkaninku ba yara ba ne."
Ya juya ya dubi inda yake zaune cikin nutsuwa ya furta." Ranka ya dad'e kamar yadda dai na gaya maka da farko cewa wannan yarinyar marainiya ce mahaifiyarta 'kanwata ce ni kuma a matsayin uba nake a wurinta. Don Allah ka ri'ke ta amana domin babu wani dalilin da zai sanya ka aureta cikin sutturarta ka dinga dora ayar zargi a kanta. Koda a gidan karuwai ka auro mace yana da kyau a ce daraja ta aure ya sa ka mutuntata  to ballantana Amina da tun tasowarta a nutse take duk da irin jarabawar rayuwar da ta fuskanta a baya hakan bai sanya ta sarayar da mutuncinta ba. Sanin da na yi mata ita din za'kwa'kwa'kura ce mai himma da zuciyar neman na kanta amma ba a ta'ba yi mata shedar banza ba. Matarka ce idan da rabo watarana za ta zama uwar 'ya'yanka don haka muna neman wannan alfarma a wurinka a matsayinka na mai nisan shekarun da suka fi nata a duk lokacin da ta yi maka lefi  wanda ba ma fatan haka sai ka kira ni a waya ka gaya mini, ni kuma zaka ga yadda za mu kwashe da ita. Maganar gaskiya Alhaji Tajo idan Amina ta sake aikata maka wani lefin makamancin wannan ka sake d'aukar matakin da shari'a ta haramta zahiri ni zan shige mata gaba ko'ina domin a a kar'ba mata hakkinta." Shiru ya ratsa d'akin kafin ya sake nisawa babu wata fargaba bare shakku ya cigaba da maganarsa. "Sannan Kuma sai abu na gaba, a madadin ni da mahaifinta da sauran 'yan uwana
Muna sake baka ha'kuri bisa abinda ta aikata maka ta yi kuskure zahiri wanda ko waye a ka yi wa hakan ba a kyauta masa ba, yadda ka ce ka yafe mata a gabanmu, Allah Ya sa hakan take a zuciyarka yanzu zan sanyata  ta sake baka ha'kuri domin tabbas yin hakan shi ya dace da ita, tunda gabad'ayanmu maslaha da kwanciyar hankali muke nema.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*70*
Jikina ne ya yi sanyi jin abinda yake ce wa, na yi shiru tare da sake yin k'asa da kaina ina jin Dada tana ce wa." Kuma ka rufa mata asiri baka tona mata ba, Allah Ya yi maka albarka mun gode sosai ka ji ko, Allah Ya saka da alheri, don Allah kada ka sanar da iyayenka da 'yan uwanka saboda kada su tsaneta a zahiri kowa zai ga ta yi maka mugunta tunda ita ai tana da yara da wani namijin, kaine abin tausayi da jaje, mun gode bisa rufe maganar da aka yi Ubangiji Allah Ya shi maka albarka."
Sai ta fashe da kuka ta sa gefan mayafinta tana share hawaye cikin kukan take ce wa." Uwarki tana kwance a kabarinta amma nasan a dalilin wannan zaman sai an tasheta ta ji abinda ki ka aikata, ai ita biyayyar aure ce ta kasheta ba ta ta'ba sa'bawa ubanki ba har ta koma ga Allah, ga Yagana nan tunda take da mijinta shekara da shekaru bai ta'ba kawo mana 'kararta ba, sai ke ko Amina, dama ai Yagana ta gaya mini kin ce badamuwarki ba ce don a lissafa miki aure, ai ba a kanki a kafara ba, to wallahi ba za mu yafe miki ba idan har ki ka sake kashe wannan auran, babu mu babu ke."
Baban Saude dariya ce ta kama shi jin irin zantukan da take yi ya ce ." Ai magana ta riga ta kare Dada menene na kuka kuma, babu wani dalili da zai sanya a tashi uwarta daga makwancinta, in sha Allahu ta nan lafiya lau kamar yadda muka je muka rufe ta, tana cikin rahamar Allah."
Ji na yi zuciyata ta tsinke dalilin kukan da Dada take shar'ba wanda na tabbatar da ce wa mikin da ya jima da warkewa daga zuciyarta ne a ka fama mata, dama duk lokacin da ake yin wani taro a family dinsu sai sun yi kuka idan suka tuna da ita. Wannan lamarin da yake faruwa ne ya tayar mata da hankali ya sanya take ti'kar kuka kamar yanzu aka yi mata mutuwar.

Kuka na dinga yi a hankali ina jan hanci. Can kasa na ce." Baban Saude in sha Allahu babu abinda zai sake faruwa wannan al'kawari ne na yi maka zan yi iyakacin bakin kokarina akan abinda ka ce mini." Na yi shiru tare da sake jan majina na dubi wajan da yake zaune wanda kaf hankalinsa yana kanmu ni da Dada, da alama kukan da muke yi din ya fara sosa masa rai na ce." Don Allah ka yi hakuri in sha Allah ba zan sake aikatawa ba, sannan kuma ni ma don Allah ka yi mini adalci ka zauna da ni lafiya ka daina 'kullacina idan na yi maka wani abin yin hakan shi yake k'ara tunzura mini zuciyata, har na aikata abinda baka so."

A nutse ya furta." Kada ki damu magana ta shige in sha Allahu rabbi, za ki shirya tare za mu koma kamar yadda na yi wa Baban Saude bayani ai babu amfanin zaman tunda an sasanta mu ko?"
Baban Saude ya ce." 'Kwarai kuwa, ai ko ba ka furta hakan ba dama ni ma niyyata kenan na ce ka dauketa ku tafi, shine abinda ya dace."
Ya gyada kansa a tsanake ya sake duban Dada da take ta faman yi masa godiya sai ka ce wadda ya yi wa gagarimar kyauta, ita godiyarta yadda ya sakaye sirrin bai tona ba, har ma mahaifiyarsa bai gayawa ba.
Ashe godiyar da take yi zata sake ru'banyuwa domin kuwa kyautar kujarar umara ya yi musu ita da Baban Sauden. Shi kuma Babansu Fadila ya yi masa

alkawarin bashi zungureriya mota domin fad'ad'a harkokinsa na sufari. Ashe kafin na shigo sun jima suna tattauna al'amura na rayuwa anan ya fahimci yana buk'atar tallafi domin cigaba da gudanar da sana'arsa.

Dama wajan kyautar ban girma ai ba daga nan ba, mugun kirki ne da shi tare da yin irin kyautar bazata wadda Allah yake so. Shi kansa Baban Saude da yake abin ya zo masa a bazata kasa rufe bakinsa ya yi, ya yi masa godiya sosai tare da addu'oi masu yawa. Na ji dad'i kwarai da alherin da ya yi musu hakan ya kara goge takaicinsa dake cikin zuciyata kuma ba ni damar yin jayayya dole na bi umarni kamar yadda suka buk'ata bayan isha'i na hada kayana tsaf Salmanu ya fita da akwatinana ni kuma na tsaya yi wa matan gidan sallama da godiya Sayyada tana fad'in in sha Allahu za ta zo mini ta yi mini kwanaki.
Muka rabu cikin kewar juna da kuma mutunta juna.
Ashe tare suke da Sukairaju yana jikin mota a tsaye yayin da shi Yallabai din da Baban Saude suke tsaye a bakin kofar gidan suna magana. Babansu Fadila ya tafi ina tsammanin. na dan tsaya a hankali na ce." Baban Saude shikkenan za mu tafi na gode sosai Ubangiji Allah Ya kara girma, Allah Ya saka da alheri."
Ya ce." Amin suma Amin Amina, Allah Ya sauke ku lafiya, ki kula ki kuma ki kiyaye da kyau."
A hankali na furta." In sha Allahu rabbi. Da sauri na yi gaba jin kuka na nema ya k'wace mini. Kafin na kàrasa bakin motar Sukairaju da saurin gaske ya bude mini na shiga na zauna ina goge hawayen da suka fara zuba a kumatuna.

Kaina a kasa Sukairaju ya bude masa kofar motar ya shigo a tsanake yana tattare babbar rigar da take jikinsa. Ya zauna sosai kusa da ni yayin da 'kamshin da yake fita daga jikinsa ya game motar gabad'aya Lumshe idona na yi a hankali na bude tare da sauke ajiyar zuciya a hankali da jin fargaba da fad'uwar gaba kad'an kad'an. Wani iri yanayi na fara ji a tattare da ni, na tashin soyayya tare da kewa dalili kuwa shine dama tun fil'azal k'amshin da ya zauna a jikinsa yana daya daga cikin abinda yake saurin tayar mini da hankali.
Jikina na d'an janye hankali na had'u da jikin motar domin ina ganin kusancin da yake tsakaninmu shi ma yana taka muhimmiyar rawa. Sukairaju ya d'an juyo a nutse ya ce." Sir za mu wuce hotel din da muka sauka ne?"
Ya gyad'a kansa a yayin da yake d'an gyara zamansa a gefana ya ce ." 'Kwarai kuwa ai tafiyarmu sai gobe tukkuna dole nan d'in za mu kwana."
Sai ya juya da sauri ya cigaba da jan motar cike da bin umarni.
Shiru ya ratsa tsakaninmu babu wanda ya dubi juna.
Kiran da ya shigo wayata shine ya ratsa shiru da ya ratsa. Ya dube ni a hankali wànda tun shigowarsa motar bai yi mini irinshi ba amma bai ce mini komai ba. Na d'auki wayar dake saman cinyata tare da duba mai kiran anti Yagana ce. Numfashi na sauke babu kuzari na sanya wayar a kunnane ban san kuma mai take tafe da shi ba, yanzu har fargaba nake yi naga kiranta.

" Kina ina yanzu?" Abinda ya fito daga bakinta kenan, ko amsa sallamata ba ta yi ba. A takaice na ce." Ga ni a mota tare da Yallabai za mu tafi."
Ajiyar zuciya ta sauke a hankali ta ce." Na so a ce kin zo nan domin akwai taimakon da na sanya a ka yi miki rubutu ne da tofi."
Shiru na yi tare da d'an satar kallonsa sai na ga hankalinsa yana kan wayarsa Allah Ya sa ma ban bud'e handsfree ba amma dai duk da haka ina fargaba saboda yana da kaifin ji, itama anti Yagana tana da matsala wallahi.
Na ji tana fad'in." Kun jima da tafiya ne, amma dai ba yanzu da daddaran nan za ku d'auki hanyar abuja ba ko." A takaice na ce." Sai gobe haka na ji yana cewa yanzu za mu nufi masauki."
Ta ce." To shikkenan zan kira ki da safe za mu yi magana in sha Allahu rabbi.

Wannan littafin na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

"To, kawai na iya ce mata na kashe wayar tare da d'ora ta a saman cinyata. Anti Yagana rigima kenan yanzu da ta tabbatar da cewa an sasanta zan koma ta daina hantarata.
Shiru ya cigaba da wanzuwa a motar shi Sukairaju yana can yana abinda yake gabansa. Ni da shi kuma kowa girman kai ya hana ya yi wa d'an uwansa magana.
Lokacin da aka kira wayarshi ban kalleshi ba amma gabad'aya hankalina yana kan saurarar maganar da yake yi a waya. Matarsa ce Hajiya Maryam ta kira shi. Na yi shiru mamaki da tsoro yana shigata. Yadda yake kashe murya da tausasa harshe wajan mayar mata da amsa shine abinda ya fi d'aukar hankalina. Jikina ya shika k'warai da aniya domin abinda yake yi ko saurayi dan shekara ashirin da biyar albarka. Idan ni na zama towon tushe ai ya ji nauyi da kunyar Sukairaju domin yaronsa ne a ganina bai kamaci ya saki baki yana fad'in wasu manyan kalmomi na soyayya da turanci ba.
Duk yadda na yi wajan ganin na ji a hakan ba komai ba ne a cikin zuciyata kasawa na yi don sai nake ganin kamar ma da gayya da cin fuska yake yi mini hakan. Da ta kira shi sai ya gaya mata yana uzuri a ganina bai kamata ya biye mata ba tunda dai ta san muna tare sai dai idan bai gaya mata cewa bikona ya zo ba, tunda duk yawancinsu munafukai ne ba su ta'ba yarda su fito da ainihin abinda yake kasan zuciyarsu.
Ban san lokacin da na ja tsaki mai tsayi ba na dan gyara zamana tare da cire gefan rigarsa da ya had'u da mayafin da yake jikina.
Had'e fuska na yi sosai a karo na biyu na sake yin wurgi da gefan babbar rigarsa da ya sake sauka a cinyata a dalilin gyara zamansa da ya yi. Sai ya juyo yana kallona still da wayar a kunnansa bai katse ba. Ban yarda na hada ido dashi ba amma yanayina kad'ai shi ya nuna a kusa nake wata'kila kiris nake jira na fashe. Kuma haka din ne don abinda nake ji a can kasan zuciyata ni kaina ya shallake tunanina.
Ya kashe wayar tare da ajiyeta a saman cinyarsa kamar dai yadda na ajiye tawa. Sai ya d'auki gefan babban rigarsa ya d'ora a cinyata yana d'an murmushi amma bai ce komai ba.

Zumbura baki na yi tare da kawar da kaina nasa hannu na cire rigar daga jikina.
Sai ya sake mayarwa yana sake matsowa jikina. A hankali murya can kasa ya furta." 'kyan'kyamina ki ke yi Amina."
Shiru na yi ban tanka masa ba, kuma ban kalleshi shi ba. Sai ya d'auki hannuna da yake ajiye a saman cinyata ya had'e yatsunmu waje daya ya rintse can kasa da karamin sautin da ni kadai zan iya ji ya furta." Mu 'kulla alkawari." Hucin numfashin maganarsa ya sauka a gefan fuskata. Ya sake matse yatsun da k'arfi yana sauke ajiyar a zuciya ya furta." Kin ji Hajiyata."
Cikin wani irin yanayi na dube shi. Duk da idanuwansa rufe suke da gilashi hakan bai hana ni fahimtar halin da yake ciki ba.
Ban iya ce masa komai ba na janye idona daga kallonsa zuciyata na d'an yi mini zafi kad'an domin sai nake ganin kamar akwai raini a lamarinsa ai ya kamata a ce yanzu ba shi da lokacin kowa sai nawa tunda mun jima ba ma tare a ganina bai kamata ya tsaya wata mace ta kira shi koda matarsa ce din ya biye mata da zantukan soyayya ba.

Ya sake furta." Mun yi al'kawari ko Amina."
Da 'kyar na ce." Ai mun yi tun a gaban Baban Saude."
"Wani nake so mu sake yi ni dake kawai, kin ji rabin rayuwata." Na dube shi da sauri jin abinda ya furta wai rabin rayuwarsa. Lallai ban yarda ba idan har ni din rabin rayuwarsa ce ai ba zai dinga yin nesa da ni ba duk tsaurin lefin da na yi masa.
Ganin na'ki biye masa ne ya sanya ya rabu da ni, a haka muka isa kasaitaccen hotel din da sai wane da wane, yana ta tsokanata ya d'auki gefan rigarsa yasa a jikina ni kuma bana gajiya da cirewa
Na ce da Sukajiru ya shigo mini da akwatinana dole akwai abinda zan buk'ata kafin na kwanta sai na yi burush da kuma kayan baccina a ciki. Idan ya so gobe idan za mu tafi din ya kuma kai su motar tunda na tabbatar da cewar tafiyar jirgi za mu yi sai dai har yanzu ban gama tabbatar da cewa ina zai kai ni ya ajiye ba legos din ne ko Abuja.
Tunda na yi wanka na fito yake ta bina da kallo don da kyar ma ya iya tashi ya je ya yi nasa wankan ya fito babu riga a jikinsa sai dogon wandon kayan da ya cire ya zauna kusa da ni a gefan gado lokacin muna magana da Sahura ta Whasap ina gaya mata sai ta kwantar da hankalinta auran bai mutu ba ga ni ma yanzu a tare da shi a d'akin hotel.
Ganin ya zauna kusa da ni ya sanya na kashe data tare da ajiye wayar a gefe, Ina kallonsa ya d'ebi nasa wayoyin duka ukun ya kashe su, ban ce masa komai ba a hankali dai nake nazarinsa yanayinsa kadai ya gama fahimtar da ni halin da yake ciki. Ai na d'auka har yanzu da dokin amarcin a tattare dashi to mutumin da yake da amarya irin haka, ni kuwa zan d'an jarraba shi na ga ni saboda nasan babu wani dalili da zai hana shi 'kin kwanciya da ni a irin wannan yanayin da yake ciki.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN✍️*

*68*
Wajan ya yi tsit kowa ya yi shiru yana sauraransa. Ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Tun kafin ta zo nan ta gaya mini halin da take ciki a waya da kuma ta zo ta sake jadadda mini duk abinda ya shiga tsakaninta dashi da abinda ta aikata masa da matakin da ya d'auka akanta. Dan Kuskure ta yi kuskure kuma ban goyi da bayan ta sake aikata hakan ba ko bayan raina na gargad'eta domin hakan fasadi ne mai girma. Ta kar'bi lefinta ta yi nadama ta tuba ga Allah kuma ta nemi gafara to me zai sanya ba za a yafe mata ba. Wannan sune kadai matsaltsalun Amina, kuma na ja kunanta kwarai da gaske akan ta gyara ta kiyaye a gaba. Ba wai ina goyon bayanta ba ne a yanzu ta ce ba ta da ra'ayin zama dashi cikinmu babu wanda ya isa ya yi mata dole domin kuwa ita ba yarinya ba ce ta san abinda yake mata ciwo sannan kuma tana da hujja ko a gaban alkali za ta fad'a masa dalilinta na son rabuwa da auransu saboda matsalar rashin daidaituwar jini da za a samar da yara masu ingantaciyar lafiya. Abu ne ya zo a zamanance ba mu ce za mu yi wa Allah wayo ba, amma zahiri lalurar nan akwaita dalilin da ya sanya ma kenan aka fara d'aukar matakin kare kai daga riskar abinda zai faru bayan an yi aure. Amma fa wannan bayanin nawa baya na nufin cewa ina goyuwa da bayan yahudawa ba ne a a ko daya domin kuwa ni kaina a lokacin da na auri iyalina babu gwaji na jini kuma ga yara na nan duka mun haifa lafiyarsu lau babu wani mai lalura daga ciki. Saboda haka Dada ki fahimce ni anan wannan ga'bar kada a tilastawa yarinyar nan a ce dole sai ta cigaba da zama da bawan Allan nan alhalin bai san girma da mutuncin ba."
Dada jikinta ya yi sanyi sosai duk karsashin da ta shigo dashi gidan babu shi a tare da ita a sanyaye ta ce." To yanzu na ji abinda kace Haruna, amma ya za ka yi ka hadu da mijin nata kasan dai shi ba yaro ba ne idan ma ka girme shi ba yawa kuma sannan ba irin mazajen yaranka ba ne da kasa ba yi musu tsawa da gindaya musu sharad'ai."
Dariya ya yi irin ta manya a tsanake ya furta." Ai na girme shi Dada, kuma yana auran 'yata duk kudi da wani abinda yake ji dashi ya zame masa dole ya ajiye a gefe guda kafin ya tunkaro inda nake muddin yana so mu daidaita. Ni wani kudinsa ba zai rud'a ni ba, ke kan ki kin san da wannan Dada."
Wani irin sanyi na ji ya sauka a zuciyata ta yi fes lallai Baban Saude ya shirya kare mini mutuncina.
Ya dubi anti Yagana babu fara'a ya ce." An ce yana kiranki a waya to na gargad'eki duk lokacin da ya sake kiranki akan lamarin ki ce masa ya nemi inda nake kuma ki sanar dashi daf nake da komawa wurin neman abincina

domin ina sa ran a satin nan da za mu shiga asabar ko lahadi zan tafi muddin kuwa ya bari na tafi bai neme ni ba to sai na dawo kuma"

Cike da damuwa da kar'bar umarni ta ce." To shikkenan in sha Allahu don d'azu ma mun yi waya da shi har yana sake jadadda mini cewa shi bai saketa ba bayan wanda ya yi mata a baya shi kad'ai ne  ya san wànda ya yi har yanzu akwai sauran igiyoyin auransa biyu a kanta."
Gyada kansa ya yi yana gyara zamansa ya ce." wannan kuma abinda ya shafe shi ne, ki yi dai yi kokarin bin umarina idan ya tuntubeki akan matsalarsa ki ce masa ya nemi inda nake domin kuwa matarsa tana hannuna."
Ta ce." To in sha Allahu rabbi."
Kwanan farinciki na yi a ranar saboda irin tsayuwar da Baban Saude ya yi akaina na ji dad'i kwarai da aniya kuma na yi masa addu'ar samun lada a wurin Allah.

***
To kwana uku a tsakani zuwansu Anti Yagana da safe ina bacci Sayyada ta shigo tana tashina wai Baban Saude yana kirana. Da zullumi na tashi na fita na wanke bakina sannan na nufi d'akinsa da yake can gefe da tsakargidan na yi sallama a nutse na shiga yana zaune da tukunyar shayi da mangal a gabansa ya gama dafa shayin yana tsiyayawa a kofi. Na sake gaisheshi duk da cewar d'azu kafin na kwanta mun gaisa. Ya amsa yana d'an motsa shayin da cokali kafin ya dube ni a tsanake ya ce." Jiya Yagana ta kira ni a waya ta gaya mini mijinki ya bu'kaci da a bashi lambata shine take neman izini na ce ta bashi  babu komai to shine yanzu nan ya kira ni a waya yake gaya mini cewa yana nan tafe gobe juma'a komai dare zai shigo akan maganarku shin ya kike gani. Ni ba zan yi miki dole ba fa Amina domin kuwa ba kowane yake zaune da mutumin nan ba sai ke, idan har kin ga da 'kwara da cutarwa a ciki to  ni don na ce masa ya sawwa'ke miki ba abu ne mai wahala ba a wajena. Idan kuma kin ga kina so ki cigaba da zama dashi sai  a ja masa kunne  tare da gargadin wannan ya zama na farko ya kuma zama na 'karshe idan har bai daina ba a gaba sai a d'auki matakin rabuwa ko yana so ko baya so tunda akwai al'kalai, shari'a kuma tana kan kowa da mai kud'i da kuma mai mulki.
Shiru na yi ina nazarin maganarsa. Babu shakka Baban Saude ya cika jarumin namiji domin kuwa abinda ya yi a yanzu ba kowanne zai iya yi ba dalili shi wanda za a titsiye din mutum ne wanda Allah Ya wadatashi da farcen susa ya kuma rataya masa taguwar arziki.

Na ce." Baban Saude idan har na rabu da auran mutumin nan duniya za ta zage ni. Sannan anti Yagana za ta 'kullece ni tunda har yanzu ta kasa fahimta. Ga 'kawata aminiyata Sahura mun samu matsala da ita duk ta dalilin haka. Zan cigaba da hakurin zama dashi muddin an nuna masa cewa abinda ya ke yi mini ba daidai ba ne, idan har ya gyara kuskuransa ni kuma na yi maka al'kawarin in sha Allahu rabbi zan yi kokari wurin ganin mun

zauna lafiya, kuma zan kiyaye abinda zai sake kawo sa'bani a tsakaninmu kamar yadda ka yi mini nasiha."

Gudun aure littafin kudi ne kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya jima yana kallona kafin ya gyada kansa a nutse ya furta." To Allah Ya yi miki albarka, ya kuma kare faruwar hakan anan gaba, sannan kuma ki yi amfani da duk shawarwarin dana d'ora ki akai, kina kallon yadda iyalina suka karanci halina tsaf to sai mu jima wata matsala bata gifta mana ba suna bina a yadda nake so, ni kuma ba na zalintarsu daidai gwargwado ina sauke hakkin kowacce. Ina so ki yi koyi dasu a dan zaman da ki ka yi tare dasu, ki d'auki darasi na zamantakewa tunda kina da abokanan zama to sai ku zama 'yan uwan juna, ku taimaka juna, ku ha'de kan yaranku waje daya, kada ku yarda wata 'baraka ta raba zumuncin yaranku a gaba za ku yi alfahari da haka. Sannan kuma kada ki kara samun ciki ki zubar wannan maganar na nanata miki ki ri'keta da kyau domin ba ke ki ke rayawa ba, haka zalika ba ke kike kashewa ba, tunda har kin yarda za ki cigaba da zama dashi a hakan to Ina yi muku fatan alheri Ubangiji Allah Ya sa har karshen rayuwarku wata matsala ba zata sake faruwa ba."
Hawaye na ji sun ciko idona saboda tsananin mutuwar jiki. Wato ana zaton wuta a ma'kera ashe Baban Saude mutumin kirki ne na gaske ban sani ba, lallai anti Yagana da mutanan da suke masa wani irin kallo sun d'auki alhakinsa domin kuwa mutum ne nagartacce mai mayar da d'an wani nasa, irin wad'annan mutanan masu tsage gaskiya da gudun abin duniya sun yi 'karanci a wannan duniyar.

Ina komawa d'aki anti Yagana ta kira ni a waya na daga tare da jin d'an faduwar gaba domin kuwa ban san dame take tafe ba. Sama sama ta amshi gaisuwa kafin ta fara gaya mini dalilin da ya sanya ta kira ni a waya. Na ce mata ai yanzu ma Baban Saude yake sanar da ni komai. Sai ta ja tsaki da alama har yanzu ciki take da ni don dai na yi mata nisa ne babu yadda za a yi ta zo inda nake ta huce fushinta saboda sanin halin maigidan , shiyasa haushina da take ji ya sake ninkuwa. Shiru na yi Ina saurararan duk maganganun da take yi uffan ban ce mata ba domin Ina iya yin magana ta ce na yi mata rashin kunya domin mu rabu lafiya duk abinda ta ce mini sai na ce to, ta kashe wayarta bayan ta gama gaggaya mini maganganun da ranta yake so da sunan jan kunne da gargadi akan zuwan da zai yi har tana cewa tasan ba ni da mutunci za a iya had'a baki da ni a wulakantashi da tozarci saboda yin hakan a wurin Baban Saude abu ne mai sau'ki dalilin da ya sanya ta kira ni kenan ta gaya mini sun yi waya dashi tun jiya kuma ya tabbatar mata da cewa da zummar sulhu zai zo.

Ajiyewar wayar na yi raina fes cikin zuciyata na ce da ke dashi dukkaninku ba kwa son gaskiya, ko yanzu ai na tauna tsakuwa don aya ta ji tsoro, na d'auka

ai girman kai ba zai bar shi ya tako kafarsa ya zo ba, ai na ji dad'i mutuka da gaske da yadda Baban Saude yake da kafiya da dagiya akan ra'ayinsa. Duk da kwarjini da haibar da yake da ita ina da tabbacin hakan ba zai firgita Baban Saude ba dalili shi ma mutum ne mai ra'ayin rik'au kuma mai tattare da wadatar zucci.

Washe gari da safe bayan mun karya kummalo na koma na kwanta bacci mai nauyi ya d'aukeni ko kadan ba na tare da wata fargaba ko zullumin abinda zai faru idan ya zo garin shiyasa kwata-kwata ma ban sanya abin a raina ba don ni har so nake ma ya zo din naga yadda za ta kaya wannan shi zai nuna mini cewa yana sona da gaske ko kuwa duka karya ce da yaudara.
Sai wajan daya na rana na tashi rana gatse-gatse ina fitowa tsakar gidan da zummar wanke bakina da burushi na sami matan gidan suna ta aiki na yau na daban ne domin Sayyada na hanga a can cikin kicin ta dasa kujera tana ta suyar kaji. Mama tana gyara alayyahu ita kuma anti amarya tana tace zo'bon da yake kan wuta.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*71*
Abinci muka ci a tare hankalinsa duk rabi yana kaina don ma ni ce karfin cin abinci. Da ga karshe sai ma ya ajiye cokalin hannunsa yana fad'in shi dan gargajiya ne bai saba da wannan ciye ciyen ba. A nutse na ce ba sai ka sanya a kawo maka abinda ka ke so ba?"
Ya yi shiru bai ce komai ba can kuma sai ya ce." Amma na ji dadin towon nan da aka sauke ni da shi a gidan kawunki Baban Saude mutumin kirki ne Amina.
Murmushi na yi kad'an amma ban ce masa komai ba.
Shiru ya dan ratsa d'akin a kafin a hankali na ji ya kira sunana. Na daga kaina na dube shi a tsanake ya furta. Da gaske fa nake da na ce miki mu d'aura alkawari."
Ina tauna abincin da ya rage a bakina na ce." Ai ban fahimci alkawarin da ka ke nufi ba.
Zamansa ya gyara babu alamun wasa a fuskarsa ya ce." Tsakanina dake babu cuta babu cutarwa duk rintsi duk wahala kada ki zauna da ni da wata zuciya ki amince da cewa ni mai 'kaunarki ne ba kuma zan cutar dake ba, wallahi tallahi Amina da wata ce ta aikata mini abinda ki ka yi mini ba na tsammanin zan sake had'a numfashina da ita. Domin ke idan ba kya ganin

abinda ki ka yi a matsayin ta'addanci da yankan k'auna ni ina gani, domin kuwa abin ya jima yana yi mini ciwo a zuciya." Ya yi shiru yana kallona jin ban ce komai ba sai ya nisa ya cigaba da ce wa ."
Babu ruwana da terere da surutun mutane, ina k'ara gaya miki da wata ce bake ba sai duniya ta ji mu da ita, duk yadda na kai ga boye sirrina da rashin son yamadidi akan lamarina wannan ba zai hana ni yin hukunci ba bayan irin wanda na yi miki, to sai
Allah Ya ragewa aya za'kinta ke ce Amina wadda zuciyata take yi wa mahaukacin so. Ina sonki wannan kowanene zai shaida haka, kuma ina da burin gama rayuwata dake, ina da burin tara zuria dake koda duka za su kasance miskinai marasa mamora masu dauke da lalurar da kike kyama. Ni ina sonsu. Ya sake yin shiru na wani lokaci kafin ya cigaba da cewa." Kamar yadda Kawunki ya fad'a na sani a zaman aure dole akwai kuskure dole kuma a samu sa'bani amma ina so ki sani sonki da kaunarki ne ya sanya mini wani ciwo mai wahalar magani a zuciyata. Wannan zafin kishin da zargin da nake nunawa a kanki ba yin kaina ba ne Amina zuciyatace, na sha gaya miki ni mutum ne mai kishi da tsantsami a duk lokacin da na tuna cewa ba ni ne namiji na farko da na fara saninki a matsayin 'ya mace ba zuciyata tana yi mini wani irin ciwo wannan shine dalilin da ya sanya nake kasa sarrafa kaina, amma in bacin haka ai nasan wacece ke tun kafin aure ya ratsa tsakaninmu had'uwarmu ta farko na bijiro miki da wani lamari wanda hakan ba dabi'ata ba ce, na yi da manufar samun dace da macen aure mai tsoron Allah da gudun abin duniya. Kin fi kowa sanin ibtila'in rayuwar dana fuskanta dangane da matayen dana aura wanda da yawa mutane suka fara dora ayar tambaya a kaina. Auranki shi ya korar da wannan rud'anin ki ka yi hakuri ki karbe ni a haka da wasiwasin za ki mutu ko kuma za ki rayu. Wannan sai ya bawa sauran mata damar kawo mini hari da sunan soyayya tunda ai kin rayu tsayin shekara ba ki mutu ba. Amina in bacin Hauwa 'yar uwata ce, kuma ina gudun 'bacin zumunci da babu dalilin da zai sanya ni na aureta tunda a can baya ai guduna ta yi saboda kada ta rasa rayuwarta kamar yadda 'yar uwarta Samira ta rasa tata rayuwar. Aurena da Hajiya Maryam kuwa wannan cikasa wasiyyar abokina na yi domin a cikin abinda yake rubuce cikin wasiyyar da ya rubuta da hannunsa kafin rasuwarsa har da neman alfarmar na auri matarsa domin cigaba da kula da ita da yaransa. Alhaji Amadu ya wuce komai a wurina domin duk yadda zan fad'a miki kirkinsa sai na rage mutum ne na k'warai mai kaunata da son cigabana. Ko ni ne na riga shi tafiya ba abin mamaki ba ne don na bashi wasiyyar ya auri iyalina saboda rufin asirinmu bakid'aya. Mu zauna lafiya don Allah, ki yi hakuri da ni, zan yi hakuri dake. A yanzu ke ce uwargina da ni da sauran iyalina muna hannunki. Muddin ki ka bud'e wata kofa ta samun sa'bani a gare mu to kin kashe kanki. Sai maganata dake ta karshe kada ki sake kaini 'kara wurin kowa domin kuwa ni ba yaro ba ne, ke ba ki ji kunyar kai mutum kamata 'kara ba Amina ke ce fa ki ka yi mini lefi kuma na yi shiru ban gayawa kowa ba amma saboda k'in gaskiya sai ki tafi ki kai ni 'kara na ji ciwon hakan sosai, kuma kin ci sa'a, ina sonki da ba zan je ba wallahi zan ta barinki da igiyoyin aurena a kanki duk ranar da ki ka gaji kya dawo dakinki."

Cikin kuka na ce." Ai kai kaso hakan, mai yasa ka'ki ha'kura, ai na gaya maka gaskiya ban 'boye maka ka dalilina ba, kuma da na fahimci na yi kuskure ba 'a yi wa Allah wayo na yi nadama na ro'ki gafararsa, kaima na ce ka yafe mini, sai ka k'ullece ni, ka dinga gaba da ni, ka rufe duk wata hanyar da kasan zan hadu da kai, ta ya ya ba zan nemawa kaina mafita ba, ai Allah ma muna yi masa lefi ya yafe mana, a lokacin ya kamata ka kar'bi tubana mu sasanta junamu ta inda babu wanda ya ji ya kuma ga ni, hakan bai yi maka ba sai kawai katin d'aurin aurenka na gani, ni ma shine dalilin da ya sanya kenan na nemi iyayena domin su kira ka su ji menene matsayin aurena."

"To mai yasa ba ki sanar da mahaifinki ba har sai kin yi tafiyayyiya kin je kin gayawa wani mutum, a ganina ai mahaifinki shi ya kamata ki sanarwa da halin da ki ke ciki Amina ba wai ki d'auko maganar ki kawota har nan garin maiduguri ba."

"Shi ma ai Baban Saude ba bare ba ne, kamar yadda ya yi maka bayani uba yake a wurina. Babanmu kuma yana da kawaici sosai bai zama lallai ya iya ce maka komai ba."
Murmushi ya yi kad'an kafin ya ce." Shi wannan din da ki ka kawo masa k'arata shi bashi da kawaici kenan."
Na dube shi da wani yanayi domin maganar tasa tana nema ta d'auki wata hanya. Sai kuma da sauri ya gyara maganar da ce wa." Yana da kirki Baban Saude amma d'an tattaunawarmu na fahimci yana da wasu 'yan matsaloli ammafa ba masu muni ba ne ainun. Na dai gaya miki kada ki sake kai ni 'kara koma wajen wanene."

Na ce." To kai ma sai ka kiyaye abinda zai 'bata mini rai, ai ka dauki alkawari ni ma na d'auka. Kuma da kake cewa wasiyyar auran Hajiya Maryam aka bar maka ai ka jima kana yi mini maganarta tare da sha'awar abinda take yi wa mijinta."
Sai ya zuba mini ido da yanayi na mamaki a fuskarsa ya furta." Kada shashanci ya sanya ki sauka daga kan abinda muke tattaunawa Amina, in banda rashin hankali daga kawai na tausaya musu ita da mijinta a lokacin da yake halin ciwo sai ki canza mini magana, wato idan na fahimceki kina so ki ce da ni tun abokina yana raye nake sha'awar auranta ko ba haka ba ne."
'Dauke kaina na yi tare da d'an zumbura baki na ce." Na ga ai itama bazawarar ce mai yasa ba ka wani shiga damuwa ba, tana fita daga takaba fa ka yi gaggawar auranta, ai ko ni ban fad'i ba haka duniya za ta sanya ayar tambaya a kanka."
Fashewa ya yi da dariya yana kallona yana yi ya ce." Mijinta da ya rasu shine ya rubuta hakan a wasiyyar da ya bari, cewa daga zarar ta fita daga takaba kada na ja lokaci a daura auren. Idan ba ki yarda ba zan nuna miki takardar idan mun je gida. Sai magana ta gaba kuma Amina ai ba ni na ga Hajiya Maryam na ce ina so ba, sannan me zai sanya ni na tsananta kishi a kanta

bayan nasan abokina ne ya aureta shi kadai ya yi tarayya da ita. Ba ki son sai da so ake kishi ba ne."
"To ai duk da haka itama 'yar kasuwa ce har fita take yi kasashen waje ta yi kwana da kwanaki ta dawo mai yasa duk hakan bai dame ka ba, idan adalci ne itama sai ka hana ta fita waje sarin kaya, sannan kuma ai yanayin jikinta irin na Samira ne siririya ce, ko ba haka kake son mace ba, ai kasha fad'a, shiyasa ka yi saurin auranta da wannan dalilin ma don ni wallahi ban yarda da wata wasiyya ba."

Ya 'bata fuska yana fad'in." Kin ga Malama ba na son rashin hankali, ke ba a zama a yi maganar nutsuwa dake sai kin soko da shirme, nasan abinda nake yi, Kuma ni tunda nake da abokina matarsa ba ta ta'ba ba ni sha'awa ba, asalima ni ne a kan gaba wurin neman auranta tare da ni dashi muka dinga zurga-zurga zuwa jos har ta zama mallakinsa. Ban ta'ba yi wa Maryam kallon wata manufa sai yanzu da kaddara ta gifta a tsakaninmu. Alh Amadu kuma ya wuce komai a wurina.

Hanci na ja, cikin takaici na ce.'' To shikkenan na ji tunda ka ce haka sai ka hana ta fita waje sarin kaya kamar yadda ka takura mini idan adalci za a yi."

Sai ya shiga girgiza kansa yana fad'in." A, a, akan me zan hana ta neman kudinta bayan a haka ta ginu, kin san yawan mutanan da suke ci da sha'a a 'karkashinta kuwa, maganar fita zuwa wata kasa wannan dama dole ta bari tunda girma ya fara hawa kanta yaranta sun fara tasawa sai ta wakiltasu, shi ma abokina yarda da cewa ba zata ci amanarsa ba ne ya sanya ya bata goyon bayan fad'ada sana'arta, kuma ke ma da ki ke yin wannan maganar ai ban hana ki kasuwancinki ba ko ba haka ba ne?"
"Ni kenan kana kokwanto a kaina shiyasa kake takura mini da zargi har da Hamusu ka dinga tuhuma har da su Allah Ya isa, ka dinga bin shafukana na intarnat kana yi mini binceka duk wani abu da na dora da zummar talla idan bai yi maka ba sai ka sanya a sauke mini, ta karfi sai da ka ruguza mini kasuwancina na media."
Numfasawa ya yi kafin ya ce." Neman rigima ne kawai irin naki Amina, abu ne a zahiri gashinan kasuwancinki dana Hajiya Maryam ya sha bam-bam, ita bata fitowa ta tallata kanta da sunan kasuwanci tunda na aureta nake bin abubuwan da take gudanarwa sannu a hankali ban hangi wani abin assha ba wanda zai janyo mana zubewar mutunci.
Ke kuma dake da kayan tallan ki ke tallatawa duniya ya ba zan d'auki mataki ba. Ko ba ni da ido da neman rahoto daga jaridu ai ina kishin kaina ba zan lamunci irin wannan business din ba, idan ba ki manta ba farko auranmu na gaya miki ki bi duk hanyoyi na halak da za su kawo miki kudi amma kada ki bi hanyar da zata janyo mini zubewar mutunci tunda kin fi kowa sanin wanene ni."

Gudun aure littafin kudi ne don girman Allah kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Shiru kawai na yi masa domin har yanzu ban gamsu da bayaninsa ba sai nake ganin kawai yana tsara ni ne saboda ban kai karfin matarsa ba ta fi ni kudi. Ita ai babbar yar kasuwace babu buk'atar  ta bi irin hanyar da sauran k'ananun 'yan kasuwa ke bi domin su kafu da kiran kostoma ta riga ta kafu ta tsaya da kafafunta.
Ganin na yi shiru ban sake cewa komai ba sai ya ce." Ni da za ki bi shawarata ma ki ajiye komai ki kama ni ki ri'ke da kyau, ni kuma duk bayan shekara daya ko biyu idan Allah Ya tsawaita mana nisan kwana na dinga baki ajiya mai girma kina haife mini. Sai ni kuma na cigaba da nema muku dukiyar tare dake da abinda za mu haifa ko."
Kallonsa kawai nake yi na rasa ma abinda zan ce. Wai duk shekara daya sai kace wata kaza yanzu da shekaru suka fara tura mini ai Allah na tuba ko zan k'ara wata haihuwar bai fi uku zuwa hud'u ba idan ma Allah Ya 'kaddara. Shiru na yi masa ban iya cewa dashi komai ba saboda Ina iya fad'in wata maganar akan maganarsa ya canza mini tawa.
Ya kai hannunsa kirjina tare da fad'in." Wannan na ga ya k'ara girma, na shiga tsananin u'kuba na rashinsu Amina."
Maganar ta ba ni dariya amma ban yi ba kawai na zuba masa ido yana matsa mini kirji dake cikin riga. Cikin zuciyata na ce dama ai dole ka shiga ukuba tunda ka saba lugudarsu yadda ranka yake so, gashi amaryartaka ba ta dasu. Hauwa da nata suka bunkasa dalilin ciki tana can wata uwa duniya ashe abin maleji ne.
Ganin ban hana shi abinda yake yi ba ya sanya ya janyo kafafuna kusa da shi ya fara kicikicin kwantar da ni a kasan kafet din da muke zaune. Na cire hannunsa tare da saurin tashi tsaye. Sai shi ma ya tashi da wani irin yanayi na tsantsar fitina ya kashe hasken d'akin ya riko hannuna muka nufi katon gadon da yake girke a d'akin. Ban hana shi tattabani ba sai da lamarin ya yi nisa tukkuna na ce masa ba ni da tsarki fa. Nan na ga gigicewa har da su rawar murya wai ban yi masa adalci ba. Na yi shiru ina kallonsa ina dariyar zucci.
Yana ta abubuwa kamar wanda ya rasa hankalinsa yana fad'in" duk ma yadda zaki yi sai kin nemi hanyar da za ki biya mini  buk'ata lallai ba zan iya ha'kuri a wannan dare ba Amina.........✍

*YAU DAI SUN YI ALKAWARI BARI MUGA WAYE ZAI FARA KARYA ALKAWARIN 😃😃😂*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*72*
'Kin rungumarsa na yi, na rabu dashi kawai wai shi dole sai ya janyo hankalina, ya riga ya san abinda yake saurin kidima ni ya mayar da hankalinsa kacokan wurin aikatawa kamar wani sabon d'an yayen da yake rikicin neman abincinsa. Sa'kon ya fara sa'bata duk yadda na kai ga basarwa sai dana gaza jikina ya fara rawa na fara
mutsu-mutsu! Tabbas na so na daure da zummar ja masa aji irin na mata amma ina lamarin ya fi 'karfina ban ma san lokacin da na tallafeshi ba a ki'dime har na so na fi shi za'kewa da kansa ya gane abinda na fad'a ba gaskiya ba ne. Sai hakan ya k'ara sanya shi sakankancewa yana buga sambatu da nishin kamar wanda ransa yake daf da barin gangar jikinsa.

Yadda muka wayi gari cikin walwala da farinciki shine abinda ya kara tabbatar mini da cewa ba a shiga tsakanin mace da mijinta domin kuwa wanda ya shiga tabbas watarana shine zai ji kunya mussaman idan ya aikata abinda zai sanya jin kunyar da gangan. Misali da ba dan Baban Saude ya yi amfani da ilimi da k'warewa wajan kawo sasanci da daidaito a tsakaninmu ba wata'kila da ya yi amfani da 'daya sigar to da ba wannan maganar ake yi ba. To shi ma sai a ka ci sa'a ya yi amfani da hikima wajan ganin ya isar da sa'kon da yake so ya isar din wanda shi ma daga 'bangaransa na fahimci abin ya yi masa ciwo sosai, kuma kamar yadda ya fad'a din na tabbatar da baya sona da buk'atar cigaba da zama da ni ba zai ta'ba bibiyata da nufin kome da sulhu ba, duk da Baban Saude bai yi amfani da tsautsauran kalamai ba, amma yadda na fahimta ya ji haushi kawai ya danne ne domin samun a zauna lafiya.Tabbas idan hakane kuwa Ina da ya'kinin zai gyara anan gaba tunda na lura ya tsani a kai shi k'ara don ko lokacin da na ta'ba Kai shi 'kararsa wurin Hajja akan lamarin Hamusu fushi ya yi da ni mai tsanani idan ban manta ba ya dinga gaba da ni sai da kyar ya sauko.

Dama tun asubahi ya ce na yi duk shirye-shiryen da zan yi jirgin karfe takwas za mu bi zuwa abuja kafin lokacin ma ya cika mun fito ni dashi a kintse Sukairaju dama tuntuni ya sanya mana kayanmu a mota.
Kafin mu isa airport din Anti Yagana ta kira ni a waya kamar yadda ta fada na ce mata ai mun riga ma mun fito muna mota zuwa filin jirgi. Sai ta ce na had'ata da shi. Ba tare da na ce komai ba na mik'a wayar tare da gaya masa anti Yagana ce take so ta yi magana dashi.
Ya kar'ba a nutse suka gaisa sai kawai ta fara yi masa godiya har ina jin yadda muryarta take rawa godiya sosai na abin alherin da ya yi wa su Dada da Baban Saude. Sai kuma alkawarin kyautar motar da ya yi wa maigidanta. Da kulawa sosai ya nuna mata cewa ta daina yi masa godiya akan abinda ya yi, ai duka an riga an zama daya don haka ba abin mamaki da godiya ba ne akan duk irin abinda zai yi mana. Ta cigaba dai da godiya dai har tana cewa dashi ya kara da hakuri dangane da zamantakewa ta dashi in sha Allahu wani

abu ba zai sake faruwa ba. Ya ce mata babu komai shi ma a b'angaransa magana ta wuce hakan ba zata sake faruwa ba.

Suka yi sallama ya miko mini wayar muka dan yi magana kafin ta katse kiran. Ya dube ni a tsanake yana ce wa." Yagana mutuniyar kirki ce sosai Amina."
Murmushi kawai na yi ban ce masa komai ba, tunanina yana can wani waje na daban. Ya gaya mini ni da Hauwa ne za mu sasanta kanmu abin nufi shine za mu raba zama. Wata shida a Legos wata shida a Abuja. Abinda yake damuna shine mai yasa ita Hajiya Maryam din ba za mu raba da ita ba, ai matarsa ce ita kamar yadda muke matayensa. Ban ga dalilin da zai sanya ya ce mu biyu ne za mu dinga wannan zurga-zurgar ba. Ba na so na yi wata magana ne ya ga kamar kishi ne ko neman fitina shiyasa kawai na yi shiru amma zahiri wannan hukuncin bai yi mini ba kuma sai na rusa shi domin kuwa ba zan ta'ba yarda ya kafa abinda nasan lallai anan gaba zai zama rikici ba.
Muka isa abuja wajan sha daya na safe. Gidanshi yana nan tsaf tunda akwai hadimai tare muka shiga amma ko zama bai yi ba ya sake fita sai zuciyata ta shiga wasiwasin akan fitarsa da gaggawa irin haka. Tun d'azu a mota kafin zuwanmu airport na ji sun yi waya da ita sai nake zargin gidanta ya nufa.
Zuciyata ta cika da takaici da b'akinciki irin yadda yake rasa sukuni akan sha'anin matar nan abinda yake yi yana nema ya wuce gona da iri ban hana shi kula da matarsa ba amma yana da kyau ya daina nuna muguwar damuwa da ita a gabana domin kuwa ba zan iya jura ba.
Ina fitowa daga wanka Yusi ya shigo. Na zuba masa ido har ya k'araso wajan da nake gefan gadon yana dariya yaro ya zama wani lafiyayye ya yi haske da kyau sai kace wanda yake rayuwa a k'etare kayan jikinsa ma abin kallone. Ya zauna kusa da ni tare da ri'ko hannuna ni kam kallonsa kawai nake yi na kasa cewa dashi komai.
Ya ce." Mama ina yini."
"Lafiya lau Yusi kai ne kuwa?" Na fad'a ina d'ago fuskarsa. Sai kece da dariya yana cewa." Ni ne mama me ki ka ga ni?"
Ajiyar zuciya na sauke a hankali na ce." Na ga abubuwa da yawa Yusi wanene ya gaya maka na zo?"
Kai tsaye ya ce." Baba ne Yana gidan Momi shine yake gaya mini tare kuke wai na zo mu gaisa." Yana rufe bakinsa Adam ya shigo da sallama a nutse ya k'araso wajan da muke jikinsa sanye da irin kayan dake  jikin Yusi. Bashi da jikin girma da alama ya d'auko jiki irin na Mamansa ya d'an risina yana gaishe ni na amsa da kulawa. Ina fad'in" Adam mai kuke bawa Yusi ya zama d'an lukuti haka?" Ai kuwa sai ya fashe da dariya yana kallonsa ya ce." Wallahi babu komai Mama jikinsa ne irin haka momi ma kullum da asuba sai ta sanya shi ya motsa jikinsa amma baya raguwa gashinan duk ya fi mu girma.
'Yar dariya na yi tare da cewa." Abinci zai rage ciki kawai idan ba so yake yi wataran  ya kasa tashi ba." Ya ce." Haka ma Yaya Salim ya ce wai sau biyu zai dinga cin abinci a rana kuma daban da irin wanda muke ci ba shine Momi

ta ce a'a, a kyaleshi 'kibarsa ta kuruciya ce yana zama saurayi zai sa'be, ba zai daina cin abinci ba."
Na gya'da kaina ina d'an murmushi zuciyata kuma cike take da nazarin irin rikon da matar take yi wa yaron ko ni dai da na haife shi albarka tunda ga zahiri nan na gani da Ido. Jikina ya sake yin sanyi sosai to ai da kunya da nauyi a ce na bijiro da wata fitinar wadda zata kawo rud'ani a tsakaninmu.
Tare suka fita da zummar zuwa su yi shirin tafiya islamiyya sha biyu na rana suke shiga su tashi shida na yamma.

Gudun aure littafin na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Shi kam maigidan ai tunda ya fita din nan bai shigo ba sai bayan la'asar wajan hud'u da rabi Ina zaune a falo cikin daya daga cikin kujerun da suke jere. Gajiya na yi da jiranshi ga yunwa ina ji a gaban idona kukunsa ya gama shirya komai a teburin cin abinci. Na tashi na je na d'iba daidai cikina na dawo falon na zauna ina cin abincin zuciyata na tunanin abin.
Shi kansa sai da ya ji nauyi da kunya a lokacin da ya shigo ya same ni, ni kadai a zaune sai tibin dana kunna.
Ya zauna a gefana yana fad'in." Amina kin ji ni shiru ko, ina can wajan Momi ne tun jiya take fama da zazzabi da mura."
A takaice na ce." Allah Ya sawwa'ke." Daga haka ban sake magana ba. Na cigaba da cin abincina cikin nutsuwa. Sai ya ce." Yusi ya shigo ko?"
"Eh Ya shigo tare da Adam.'' Ya furta." Ni ne na gaya masa ya zo ku gaisa."
Na ce." Ai kuwa ka Kyauta."
Shiru ya yi yana dan kallona da wani yanayi kafin ya ce." Mai ya faru na ga yanayinki ya canza  ko ni ne?"
Ya fad'a yana matsowa kusa da ni.
Cikin zuciyata na ce aiki ya same ka.
Shiru na yi ban ce masa komai ba.
Ya tsargu sosai don gabad'aya kin sakar masa fuska na yi. Ganin haka sai ya tashi ya haye sama. Na yi zamana ban bi shi ba domin wallahi har cikin zuciyata haushinsa nake ji. Ni ba zuwan da ya yi wajenta ne yake ba ni haushi ba yadda yake d'aukar lamarinta da muhimmanci shine abinda ya fi 'kona mini rai. Yanzu ga matarsa can a wata uwa duniya d'auke da cikinsa amma ban ji ya kira ta ba tun jiya ai muna tare maganarta ma bai yi mini ba. Amma kan wannan tsohuwar yanzu sai ya gigice.
Bai sauko ba sai daf da magariba, Ina zaune a falon ina kallon wani movies da ya d'auke mini hankali
Na hangi saukowarsa cikin jallabiya da  hula tashi kafiye naci a saman kanshi cikin shirin shiga massalaci.
Janye idona na yi daga kansa shi ma bai ce mini komai ba ya fice. Na sauke ajiyar zuciya a hankali na tashi na hau saman domin gabatar da tawa ibadar.
Ana idar da sallar ya shigo. Na lura yana so ya gyara abinda ya yi a d'azu shiyasa ya dawo da wuri.

A saman dadduma ya same ni a zaune na idar da sallar amma ban tashi ba. Ya zauna kan wata kujera mai kamar gado da take can wani gefe a d'akin. Yana fad'in." Idan kina idar miko mini Loptop dina ga ta nan a gefanki.
Ba tare da na ce komai ba na tashi na je na d'auko masa ya kar'ba tare da nuna mini wajan zama a gefansa.

Zama na yi da hijabin a jikina. Shiru ya ratsa wajan yana ta dube-dubensa bai ce komai ba. Sai da ya gama tsaf sannan ya rufe computer ya dube ni tare da cewa." Za mu je gidan Momi ki dubata ko?"
A sakarce na ce." Wacece Momi?" Duk kuwa da cewar na gane wadda yake kira da sunan irin yadda na ji yaran na kiranta da shi.
Ya ce." 'Yar uwarki mana, da gaske ba ta jin dad'i kin san zafin zazzabi da mura dai."
A nutse na ce." Mai zai hana ni zuwa na dubata, to Allah Ya sawwa'ke."
Ya amsa da "Amin."
Shiru ya sake biyo baya kafin na ce." Ya Hauwa kuna waya ko?
Da sauri ya ce." Sosai ma kuwa, d'azu nan kafin na shigo sai da na kira ta, wannan watan da ya mutu shine na haihuwarta har wani ya kama sakamakon scanning ya nuna bakwai ga wannan watan da muka shiga shine daidai lokacin da suka bada result. Sai dai kuma komai na Allah ne wata'kila ma gobe tana iya haihuwa ko.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*

*73*
Har cikin zuciyata nake jin dad'in haihuwar da za su yi domin kuwa tuntuni na yakice abinda zuciyata take raya mini game da haihuwar da za su yi, idan har ina son kaina da zaman lafiya dole na takaitawa kaina kishi akan abinda za su haifa tunda ni dai ga yadda kaddara ta zo mini. Da 'yar kulawa na ce." Hakane tunda watan haihuwar ya riga ya fita har wani ya kama cikin kowane lokaci tana iya haihuwa
don hakan ba abin mamaki ba ne a wajan Allah."
Ya ce." Allah Ya sauketa lafiya dan Annabi."
Na amsa da "Amin Ya Allah."
Sai da muka ci abinci tukkuna muka fita zuwa gidan nata.
Adam da Yusi muka samu a falon suna kallo . Na tsaya muna magana yayin da shi kuma maigidan ya nufi sama ban bi shi ba saboda bai nemi hakan ba.

Ina nan a tsaye ban kai ga zama ba ya sauko yana cewa ya ki ka tsaya anan Amina.
Ban ce masa komai ba illah ido da na zuba masa. Akan wanene dalili zan bi shi ai yana da kyau a ce ya fara shiga ya sanar mata tunda ba a san a halin da take ciki ba. Idan shi mijinta ne ni kuma fa, wata'kila hakan bai zai yi mata dad'i ba.
Bayansa na bi muna hawa benan yana sake tisa maganar wai na tsaya ina ta d'ari-d'ari na'ki sakin jikina. Na yi masa shiru ban tanka masa ba. Da dai naga ya'ki ya bar maganar daf da zamu shiga d'akin na tsaya Ina dubansa babu fara'a a tare da ni na ce ." Don Allah maganar nan ta isa haka fa, ina dalili sai maimaitawa ka ke yi, ai ba daidai ba ne kai tsaye kawai mu kutsa mata d'aki idan kai babu lefi hakan ni kuma fa, ai ba mu san halin da zamu same ta ba."
Yadda na nuna 'bacin raina akan hakan ya sanya bai sake wata magana ba muka shiga d'akin. Na yi kokari sosai wajan ganin na daidaita yanayin da nake ciki.
Tana zaune gefan gado sanya da kayan bacci masu taushi a jikinta. Wata kujera dake can gefe ya nufa ya je ya zauna shi kadai nasan ya yi hakan ne domin mafitarsa yana tsoron ya zauna kusa da wata daga cikin hakan ya zama lefi shiyasa ya ke'be kansa waje daya.
Sosai muka gaisa cikin sakewa tunda dama ita din macace mai fuska da iya hurd'a da mutane. Babu wani abu na kishi da ganin kyashi da na karanta a tattare da ita. Sai dai na hangi tsantsar soyayyarsa a cikin idanunta. Domin kuwa motsi kad'an za ta ta juya ta kalleshi ta dinga kokarin janyo shi cikin maganar da muke yi a tsakaninmu ni da ita amma ya'ki ya sake ya dai 'kyalemu muna hirarmu. Daga karshe ma sai ya sauka kasa ya bar ni tare da ita. Anan na dinga nazarinta duk da dare ne na fahimci tana jin jiki kuma murar ta kama ta da k'arfi. A lokacin sai kawai zuciyata ta dinga raya mini wani abu wai ko ciki ta samu domin sai nake ganin yanayinta kamar na mai karamin ciki. Kirjinta ya ciko ko bireziya ce oho, ni dai sanin da na yi mata zaman makokin mijinta bata da wadatattun kirji
ita kanta ma gabad'aya ta murmure ta yi ki'ba amma ba sosai ba. Sai jikina ya k'ara yin sanyi da al'marin Ubangiji. Lallai ciki ne da ita kuma shine dalilin da ya sanya duk ya gigice tunda abinda yake nema ne ya samu.
Duk da ban tabbatar da hasashena ba amma tun a lokacin na ji na fara tausayin kaina. Zuciyata ta dinga yi mini munanan tunane-tunane. Idan ma har na samu cikin na haihu yarana ne za su tashi daban a gidan masu d'auke da wata lalura idan da k'arar kwana kuma d'aya bayan daya duk su mutu.
Da wannan tunanin na kasance har muka bar gidanta daurewa kawai nake yi amma gabad'aya zuciyata ta kasa juriya sai da na buya a toilet na ci kuka na 'koshi na dinga yin istigifari da rokon Allah ya sassauta mini abinda nake ji a cikin zuciyata.
Washe gari da safe sukuku na tashi babu karsashi a tare da ni. Haka kawai abinda ba ni da tabbas akai ya ke nema ya daga mini hankali. To menene ribar auran ne haihuwa ce, mai yasa nake jin b'akinciki dan matarsa ta samu ciki. A ganina ai abin murna da farinciki ne a gare mu bakidaya, kamar yadda

nake jin dad'in haihuwar Hauwa yana da kyau itama wannan din na yi farinciki idan har hasashena ya zama gaskiya. Amma sa'i guda  na ji duk tawakkalin da na fara dangane da al'amarin ya ruguje, wani mahaukacin kishi yana nema ya zautar da ni.

Shirun da ya yi mini bai gaya mini matarsa tana da juna biyu ba shine abinda ya yi mini ciwo a ganina menene abin boye mini, idan ba yana nufin wani abu ba. Ko yana gudun ya gaya mini na ji haushi ko na nuna b'akincikina. Duk da bai zama dole a ce ya gaya mini abinda ya shafe shi da matarsa ba, amma ai idan da fahimtar juna da zama na amana ba lefi ba ne don ya gaya mini sai mu had'u mu yi farincikin tare gabad'aya.
 Na yi ta ko'karin ganin na danne damuwar da nake ciki amma ina sai da ya fahimci wani abu yana damuna.
Ya dinga bibiyata duk domin son ya ji abinda yake damuna kawai na ce masa babu komai. To ne zance masa ni ban iya 'karya ba balle na yi masa, babu kuma dad'i na fito fili na nuna jin haushina dan matarsa tana da ciki.
Kwana biyu a tsakani ya gaji da tambayata ya kyaleni kawai ya zuba mini ido tunda ya lura da cewar ba na son doguwar hira sai ya daina nema da ita. Amma baya fashin kwanciya da ni duk ranar girki na. A haka ya yi kwana biyu a wajena ya koma gidanta a washe garin ranar ya shigo da safe lokacin ma ban ma tashi ba tunda na yi sallar asubahi bacci ya d'auke ni mai nauyi. Shine ya tashe ni da farinciki yana gaya mini yanzu nan Hauwa ta haihu.
Ganin yadda yake cikin annashuwa da murna ya sanya ni dole ni ma na ara na yafa ina tambayarsa abinda aka samu namiji ne kuma gabad'aya suna cikin koshin lafiya.
Fatan alheri na yi musu gabad'aya tare da addu'ar Allah ya raya abinda aka samu. Ya kuma bada lafiyar shayarwa. Ya ji dad'i kuwa ya dinga amsawa cikin jin nishadi.
A ranar ya shirya tafiya bauchi da nufin zuwa ya je ya dawo duk a ranar tunda tafiyar jirgice. Ban damu ba tunda ba kwanana ba ne, na yi masa addu'a da fatan alheri ya tashi ya fita domin zuwa ya kintsa.

Don Allah kada ki karanta mini littafi sai kin biya ni hakkina

Sai bayan ya tafi tukkuna na shiga tunanin da na sani na kar'bi lambar wayarta a wurinsa sai na kira ta na yi mata barka  tunda rantsuwar nan da na yi tana nan ba zan sake taka k'afata garin ba sai dai duk abinda za a ce an jima ba a fad'a ba, wannan duniyar idan har mutum ya ce sai ya farantawa wani rai yana tare da wahala domin kuwa wasu lukutan ma wanda kake kokarin ganin ka bashi farinciki shine na gaba gaba wajan ganin ya jefaka a masifa. Baban Saude ba irin nasihar da bai yi mini ba akan zama lafiya da abokanan zamana, na kuma d'auki nasiha da shawararsa duk wadda ta shirya zaman lafiya da ni, to ni ma a shirye nake dana zauna lafiya da ita, amma wadda take ganin ta fi karfin ta ba ni girmana na babba a cikinsu sai ta yi rayuwarta ni ma na yi tawa.

Wannan shawarar na yanke a zuciyata wani sashe yana gaya mini cewa da duniya zata zageni hakan  zai sake tabbatarwa da masu zargina cewa ina hassada da ciki da haihuwar. Tunda ai tun farkon samuwar cikin an sha rigima da ni akan wani dalili.
Ni ba zuwan ne matsala ba a wajena ba, Ina gudun kallon banza da habaici shine kawai abinda nake tunani, ba na so a yi mini abinda zai hasalani na kasa jurewa na aikata abinda bai da ce ba.

To daga cewa zai je ya dawo a yini sai gashi sai da ya share kwanaki uku tukkuna kafin ya dawo  sauran kwana dayan Hajiya Maryam da kwana biyuna ya yi su ne a tare da Hauwa.
Ban damu ba saboda nasan hakan da ya yi shine daidai yana da kyau itama ya zauna da ita sosai domin su tattauna abinda ya shafe su.
Da daddare ya dawo wajan goma da rabi har na kwanta ya shigo yanayin dana gan shi ya nuna mini cewa ya d'an jima da dawowa domin jallabiya ce a jikinsa. A can gidanta ya sauka zai cike mata cikon kwana dayanta.
Ya zauna gefena ni kuma na tashi zaune Ina laluben hulata data fadi na mayar kaina a nutse na gaishe shi ya amsa yana yi mini wani irin kallo. Hakan ba sabon abu ba ne a wajena domin ni kaina na kan rasa me yake kallo a jikina babu dai abinda bai sani ba, babu kuma sabon abu.
Saukar hannunsa na ji  saman kirjina. Da sauri na ture ina dan hararsa. Ya sake matsowa jikina na matsa da baya
Sai ya tsaya yana kallona kafin ya gyad'a kansa kamar wadda ta yi masa mugun lefi.
Na daure tare da ce wa." Ina Hauwa da jariri suna nan lafiya?"
"Lafiyarsu." Ya fad'a yana duba wayarsa kafin ya miko mini wayar yana fad'in." Kin ga hoton jaririn."
Na kar'ba da sauri ina dubawa. Kamarsu daya wallahi, ina dariya na ce." Kamarku daya fa Baba, wannan yaron hotonka ne."
Da d'an murmushi a fuskarsa ya ce." Haka mutane suke ta fad'i Hajja tana gaisheki yaushe za ki je ne?"
Shiru na yi ban bashi amsa ba, ina ta duba hotonan yaron da yake cikin wayarsa.
Sai ya sake maimaita tambayarsa.
Ba tare da na dago kai ba na ce." Gaskiya ba zan rufe maka ba babu inda zan je."
Ya dube ni da wani irin yanayi kafin ya furta ." Akan wane dalili, mai aka yi miki?"
"Ba a yi mini komai ba." Na fad'a cikin mamakin yadda aka yi ya manta irin wulakancin da suka hadu suka yi mini har da shi. Hauwa na je garinsu cikin gidansu amma bola ta fi ni daraja suka mayar da ni abar nunawa da yi wa dariya ita da 'yar uwarta.

"Idan kuwa hakane babu wani dalilin da zai sanya ki ce ba za ki je ba Amina muddin zan bada umarni ki bi shi."

Hawaye ya ciko idona na ce ." Don Allah kada ka takura mini, ka kyaleni na ji da abinda ya dame ni, ba zan je fa domin kuwa ina da dalilina, idan kai ka manta ni ban manta ba."
Ya gyara zama yana kallona tare da cewa." Ni ban manta komai ba Amina, ki fito fili ki gaya mini abinda yake damunki ba ki zauna kina barin shi a cikin ranki ba, na lura kwana biyu nan tun kafin Haihuwar nan ba ki da walwala ina alkawarin da muka k'ulla dake?"

Hawayen dake cikin kwarmin idona ya d'igo. Na sanya hannu na goge tare da ce wa." Ai ni ban k'ulla alkawari da kai ba saboda na san ba iya cikawa za ka yi ba, kawai mu yi ta zama a haka cikin munafurtar juna."

Sai kawai ya yi sakare da baki yana kallona. Ni kuma ina ta kuka kamar wadda aka yi wa rasuwa. Gadon ya hayo sosai ya riko hannuna kafin ya ce." Munafurci na yi miki?"
Shiru na yi ban tanka masa ba. Ya ce." Ki tona mini asiri kawai ba wai ki dinga b'oyewa ba, ki gaya mini hak'kinki dana take tun zuwanmu nan, ashe duk takatsantsan din da nake akan kada wadda ta zarge ni a cikinku wato hakan bai yi miki ba, kina yi mini wani irin kallo."
Hanci na ja, na cire hannunsa da yake cikin nawa na ce." Idan zaman gaskiya da amana muke yi menene na 'boye mini matarka tana da juna biyu, ai na gane nufinka kada ka gaya mini, na ji haushi ko na yi mata hassada ko?"
Da wani irin yanayi ya furta." Wace matar tawa ce take da ciki?"
Kallonsa na yi, muka had'a ido, sai na d'auke kaina ban ce masa komai ba
Yasa hannu ya dago kaina ido cikin ido ya ce." Ki gaya mini wacece take da ciki."
Na ce."Amaryarka?"
"Ita ta gaya miki tana da juna biyu?"
Shiru na yi domin ba ni da amsar da zan bashi sai na ce masa alamar hakan na gani. Sai a lokacin ma na fara jin kunya da nauyin abinda nake yi wanda hakan zai sanya shi saurin gano cewa kawai zafin kishi ne yake damuna...✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*74*
Ya jima yana kallona jin ban bashi amsar da ya tambayeni ba sai ya gyad'a kansa a nutse ya ce." Ni ne dai mijinta Ina ganin kafin ta gayawa kowa tana da juna biyu ni za ta fara gayawa, amma tunda maganar ta fito daga bakinki

tabbas nasan ba 'karya ba ne, zan je na tambayata na ji dalilin da ya sanya ta 'boye mini abina."
Ri'ke hannunsa na yi a sanyaye na ce." Kada ka tambayeta don Allah."
"Akan wane dalili?" Ya fad'a cikin wani irin yanayi. Shiru na yi ban iya ce masa komai ba. Sai ya sake maimaita tambayar da ya yi mini a karo na biyu.
Na daure cikin daburcewa na ce." Ni ma fa ba gaya mini ta yi ba kawai ina hasashene."
Ya zuba mini idonsa 'kuri yana kallo. Nauyi da kunya ya sanya na yi kasa da nawa idon. Sai ya yi murmushi.
mai sauti kafin ya ce." Momi ba ta da ciki Amina, domin kuwa da tana da shi nasan ba zata rufe mini ba zata gaya mini tunda tasan abinda nake nema ne ido rufe, daga yau ki daina yanke hukunci akan abinda ba ki da tabbas akai."
Na yi shiru ban tanka masa ba, domin kuwa ni kaina nasan ba ni da abin fad'a kuma ya fi ni gaskiya to idan ma cikin ne da ita menene abinda ya dame ni.
Kamar yasan tunanin da nake yi kenan ya matso kusa da ni sosai yana cewa." Ni zan fi so ma ki fara samun cikin Amina."
Kallonsa na yi. Sai ya daga mini kai da wani yanayi ya cigaba da cewa." Momi ta kwana biyu shakararta arba'in da uku fa, ina tsammanin idan ba tsananin rabo ba a wannan matakin za ta iya wuce haihuwa don dai tana da karamin jiki ne."
"Humm." Kawai na ce masa ina nazartarsa sanin halin maza akwai wahala, sun iya dadin baki da yaudara amma in ba haka ba yaushe zai zo ya zauna yana tsara mini magana. Shekara arba'in da uku shine ta wuce haihuwa muddin tana yin jinin al'ada bai d'auke ba za ta iya d'aukar ciki.
Fuskata ya dago da hannunsa muka kalli juna sai ya matso da bakinsa daf da nawa yana so ya sumbuta gabad'aya yanayinsa ya canza da sha'awa. Ban yarda na bashi damar da hakan ba, ya gama lalube mini jiki da hannusa ya tashi ya tafi da sanyi jiki domin ga dukkanin alamu yana cikin wani yanayi na buk'ata. Bai fito ya gaya mini ba amma ina zargin ba wata cikakkiyar gamsuwa yake samu daga wajenta ba, koda kuwa ita tana gamsuwa da shi, to ta bangaransa dai sai a hankali. Ina kuma
gane hakan ne a duk lokacin da kwana ya dawo hannuna. Yakan nuna d'oki da murnarsa.

Washe gari da safe ina nad'e a gado ya shigo mini. Yanayin yadda ya shigo a hargitse ya sanya na gane akwai matsala. Na tashi zaune da sauri ina gaishe shi. Ya amsa a gajarce kafin ya ce." Ki shirya zuwa bauchi gobe in Allah Ya kaimu."
Kallonsa na yi naga babu nishadi a tare da shi. Sai na daidaita yanayin fuskata ni ma a nutse na furta." Na gaya maka fa ba na tsammanin zan je gaskiya saboda Ina gudun wulakanci, tunda a wancan karon ni na je, to mai zai hana wannan kuma ita ta je."
"Ba na son jayayya da taurin kai fa, kada ki 'bata mini rai, baki da wata hujja anan Amina"

D'auke kaina na yi ban ce masa komai ba. Ya girgiza kansa yana fad'in." Bari na kira Baban Saude na sheda masa tunda ba za ki yi yadda nake so ba."
Cikin dauriya na ce." Na fa gaya maka irin wulakancin da ta yi mini a wancan lokacin Hajiya Saratu ce kawai ta goyi da bayana, ya za a yi ka tursasani zuwa wurin da za a tozarta ni a wulakantani"
Ya zauna kusa ni a hankali." Zuciyata ba dad'i Amina, ke ma kada ki 'bata mini rai, ki yi abinda na ce dake kin ji ko, kada ki duba kowa ki duba ni Amina."
Yadda yake magana da yanayi na damuwa shine abinda ya sanya mini kasala. Na goge ragowar hawayen da yake idona na ce." Ba na gudun zargi da zagin mutane Baba, amma ina kishin kaina, kuma wasu lukutan ba ni da juriya idan aka nemi a ci zarafina sai inda karfina ya kare ba na so na je garin mutane a yi rigima da ni."
"Na fahimceki tuntuni Amina, amma ina so ki sani wannan zai zama abin zargi da gutsiri tsoma, ba na so na ji ana zaginki, ko a fadi mummunar magana akanki, duk abinda za ki yi ki yi shi domin ni kin ji matata."
Tausayi ya ba ni sosai gabad'aya a hargitse yake ga dukkanin alamu akwai abinda yake dannewa bai fito ya fad'a ba. Ni ma kuma ba zan so na ji ba tunda tsakaninsa ne da iyalinsa.
Zan je dominsa kamar yadda ya nemi alfarma, amma ba na tunanin zan kwana don ban ga dalilin yin hakan ba.
A wannan matsayar muka tsaya na ce masa ba zan kwana ba kuma sai dai mu je tare ya ce ya amince da hakan.
To na d'auka shikkenan magana ta 'kare har ya juya zai fita sai kuma ya dawo ya sake zama a kusa da ni kawai ya zuba mini ido.
Ni ma sai na zuba masa nawa mun jima muna kallonsa juna kafin a kasalance ya furta." Ba ki gane ina da matsala ba Amina?"
Na ce." Ban gane ba, ai na d'auka matsalar muka warware yanzu."

"Ke ce matsalata."
Ya fadi haka yana bin sassan jikina da wani irin kallo. Cikin zuciyata na ce ka gama zagaye-zagayen kenan, wata'kila ma ko karyawa bai yi ba ya tashi da fitina.
A nutse na ce." Ai ba girki na ba ne?"
"Na dawo hannuki tunda yau na gama yi mata kwana biyunta, kuma haka na wanzu cikin buk'ata domin ita ba ta cika lafiya sosai ba."

A hankali na ce." Lallai to ai a haka za ta saba, ni ba zan yarda mu fara 'yar haka ba gaskiya ya kamata ta zama mai juriya, tunda ni ma da haka na horu."

"Duk da haka dai ai hallitarku ba d'aya ba ce, Amina ni fa kina saurin tayar mini da hankali motsinki kadai yakan jefa ni a wani hali balle kuma na kasance a kusa dake giwar matana, kuma zinariyar gidan Tajudeeni"

Mamaki ya kama ni jin yau wanda ake yi banbad'anci shine shi ma yau wani dalili ya sanya ya shi yana yi. Na yarda namiji a gaban mace yakan zama sahorami koda kuwa mai mulki ne mai dukiya ne ko gawurtaccen malami akwai wajan da izza da jin kai basa tasiri.
Ya sa hannu ya janyo ni ya matse a jikinsa yana kyarma yake fad'in." Jiya na dauka mutuwa zan yi Amina, da tsananin bukata na kwana ki tallafe ni masoyata."
Na ce." Ni fa ka daina gaya mini sirrinka Baba, dan gaskiya ni ma ba zan ji dad'i ba idan na ji kana gayawa wata abinda yake tsakaninmu."
Hannunsa a cikin rigata ya furta." Babu ma wanda zan gayawa, to me ki ka yi mini, ni kullum cikin sanya miki albarka nake saboda Ina tsananin gamsuwa dake gimbiyata, Allah Ya ja zamaninki."
Murmushi na yi amma ba mai sauti ba na tashi daga jikinsa. Ya bi yo ni da kallo idonsa a kankance. Na ce.'" Na ji amma gaskiya ka bari sai zuwa dare a lokacin ne ka fita daga hannunta, amma har yanzu maganar nan da muke yi da kai a cikin hakkinta ne."
Sai ya tur'bune fuska yana fad'in." Wallahi ba ki isa ba, ba zai yiwu na zauna cikin lalura saboda wani lissafi na banza ba, ita ban samu gamsuwa ba da ita ba, ke kuma kawai sai na zuba miki Ido saboda Ina jin tsoronki ko."
Shiru na yi masa. Ganin haka sai ya cire jallabiyar dake jikinsa ya ajiye da sauri zan sauka daga gadon ya riko hannuna har yana murd'ewa.
Cikin zafi na ce." Zaka targada mini hannu Baba."

Kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba

Bai ce komai ba ya kwantar da ni ta karfin tsiya ya danne tare da bankare mini hannu ya rirrike da hannuwansa yana fad'in." Ku ba yara k'ananu ba ayi ta fama da ku, ki 'kwace idan kin isa, ko kin d'auka na yi tsufan da ba zan iya yi mini irin wannan danniyar ba.
Ina dariya na ce." To duk mai ya kawo haka, ka sassauta mini don Allah ka cika mini hannu ka kwalmade mini su.
Sassautawa ya yi amma bai cika ni ba, ya ce." Yadda nake ji na garau ko saurayi matashi ba abinda zai nuna mini, ke kullum idan za a neme ki, ko kina so sai kin yi jayayya haka da'biarki take Amina.
Cikin jin ciwo domin hannuna ya k'age wajan hammatata na ce." Na ji don Allah ka sakar mini hannu wannan a zabtar da ni kake yi da gangan wallahi."
Ya sake ni ya zauna gefan gadon yana kallona." Cire kayanki." Yafad'a cike da bada umarni.
Baki na zum'bura tare da juyar da kaina. Bai sake cewa komai ba sai ya sanya hannu a jikina da kansa ya tube riga da siket din material din dake jikina ya cire rigar maman ya jefar a ki'dime ya had'a ni da jikinsa ya matse yana sakin wani irin numfashi ya dinga bin ilahirin jikina da sumbata kamar zai cinyeni.

****

To kamar yadda muka tsara tafiyar abinda ya faru kenan. Mun je bauci kuma cikin ikon Allah muka dawo a ranar da muka je din. Na kuma yi mamaki kwarai da gaske da naga canji mai yawa wurin Inna Uwani da ita kanta maijegon da 'yan uwanta, sun tar'be ni sosai cikin sakin fuska da kulawa ba kamar yadda na yi tsammani ba. Inna Uwani duk ta watsar da wannan kiyayyar da take yi mini yau har tana yi mana fad'a da nasiha ni da Hauwa akan mu zauna lafiya da juna, haka zalika kuma kada mu yi zaman gaba, mu had'e kai mu zama tsintsinya madaurinki d'aya irin abubuwan da aka yi a baya kada su sake faruwa. Sosai na yi mamakin hakan. Cikin zuciyata na ce dama ai karya fure take yi bata 'ya'ya kuma duk mai gaskiya zahiri shine a sama. Abinda nake ta gudu bai faru ba, wata'kila dana biyewa zuciyata dangane da abinda ta tsara mini na shiga bakin duniya kenan na kuma zama abar kallo da tofin alatsine. Yaro tubarkalla ma sha Allahu wanda tun ranar da aka haife shi babansa ya yi masa huduba da Ibrahim Khalil sunan kakansa kenan sai uban ya ce a dinga kiransa da suna Khalil. Ya sha gata kwarai da gaske daga wajan Babanshi da abokansa kuma ni ban ji haushin duk irin hidimar da zai yi akan haihuwarsa ba, komai yana da lokaci kuma amfanin dukiyar kenan.

Ba su shirya wani gagarimin taron suna ba don maijegon tana d'an fama da ciwon kafafu da yake sun yi kumburi irin na ciki, amma suna sacewa a hankalina. Ma'aikaciyar lafiya ce ita dalilin da ya sanya ma kenan ta ce babu wani gagarimin taro da zata yi iya family dinsu ma kadai sun isa tunda suna da yawa. Hakan ma don ba yadda za ta yi ne domin wani ko ka ce masa babu suna to sai ya zo shiyasa inna Uwani ta ce dangi ba za a hana su zuwa ba, ita kuma yanayin jiki da lafiyarta baya buk'atar hayaniya saboda jininta ya d'an hau kad'an bayan haihuwar amma dai ya daidaita yadda ake bukata yanzu.
Hidima sosai ya yi musu don gaskiya ya 'batar da kudi ko ga yanayin irin mahaukatan kayan da sayawa yaron ita kanta maijegon ya saya mata sutturu sannan ya bata kud'i. Haihuwar fari ce a wajensa itama haka babu lefi a cikin dukkanin abinda ya yi..........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*75*
Da gaske dai maleji yake yi da amaryarsa domin tun yana 'boyewa yanzu a fili yake nunawa. Ita dai macace wadda ta kware wajan iya kalamai romance amma fa a shimfida sunanta sorry raguwa ce. Wata'kila hakan kuma yana da

ala'ka da rashin sabo domin kuwa kowane namiji da irin hallitarsa zata iya kasancewa tsohon mijinta ba shi da karfin sha'awa da fitina irin nasa. Shekara da shekaru ta riga ta ginu a haka, ga shekaru sun tura tana sake yin rauni gefe guda kuma ga hidindimu na yau da gobe harkokinta na kasuwanci wannan kadai ya isa ya cire mata na ci da k'ulafucin d'a namiji. Shiyasa aka ce mata suna suka tara kowace mace akwai ta inda tafi kauri akwai kuma ta inda ta gaza, wasu matan kuma duka sai ka ga Allah Ya had'a musu mazajensu suna amfanuwa dasu ta kowane sashe. Tabbas ba yabon kai ba. Ni kaina na tabbatar da cewa Ubangiji ya yi mini baiwa da ba kowace mace yake yi wa irinta ba. Bai fito ya gaya mini ba a fili ba amma na tabbatar da cewa ni ce giwa kuma zinariyar zuciyarsa da kuma cikin gidansa.

***

Kwanan Hauwa arba'in da shida da Haihuwa ya zo yana gaya mini za ta dawo amma ya nake gani domin ya bari ne ta gama wanka sai ya koma legos bayan mun yanke shawara. Na ce kawai ya bari ta zo nan 'din sai mu yanke shawara a tare domin ni har yanzu ban gama aminta da tsarin da ya yi ba, tabbas idan za mu raba wata shida shida ni da Hauwa to kuwa ban ga amfanin auransa da Hajiya Maryam ba domin kuwa idan ya ce zai biye mata akan abinda take so saboda wani dalili to kuwa babu shakka akwai gyara a cikin auransu. Ba zai yiwu a ce saboda mu kad'ai ne za mu dinga d'aukar lalurarsa ba. Itama ai matarsa ce tsakani da Allah kenan ni na yarda zan d'auki wata shida idan ya so su kuma su raba wata uku uku a tsakaninsu.

Da kansa ya je bauchi domin ya d'auko Hauwa da yaronta. Tabbas idan a da can babu soyayyarta a zuciyarsa to yanzu kuwa ba za a rasa ba, ba don komai ba sai dalilin abinda ya ratsa tsakaninmu wato yaron da suke haifa a tare. Ban ji haushinsa ba dangane da duk rawar kan da yake nunawa akanta da yaronta domin kuwa na riga na tabbatar da cewa hakan sai ta faru to damuwa da bakincikin hakan zai iya haddasa mini ciwo ne don babu wani abu da zan iya hanawa, matarsa ce kuma uwar yaronsa. Babu dalili mai k'arfi zan ce masa abinda yake yi ba daidai ba ne. A wasu lukutan ma ni da kaina nake taya shi mu had'u gabad'aya mu yi ta kallon hoton yaron wanda kamaninsa ke k'ara fitowa sak kamar ya yi kaki ya tofar.
Ranar da ta dawo tare da ita ya kasance domin gidane mai yalwa wadataccen zaman mace hud'u kuma cikin sakewa babu takura balle wata ta ce an matseta.
Washe garin ranar da ta dawo da yamma muna tare falon Khalil yana hannuna muna hira da ita cikin kulawa kamar babu wata matsala da ta taba faruwa a tsakaninmu yadda na lura ma ba ta fiye so mu had'a ido ba ko magana take yi kanta a 'kasa ko tana kallon wani waje daban a haka muke yin hirar. Cikin zuciyata na godewa Allah da bai sa na cuceta a zamantakewarmu ba abinda suka yi a can baya shine yake damunta
Towol din goyansa ta d'auko mini na goya shi a bayana, cikin kankanin lokaci bacci ya d'auke shi. Ina daga tsaye ina dan jijjigashi tana gaya mini irin

rigimar da ya dinga yi kafin su yi arba'in har yanzu bashin baccin da ta tara bai sake ta ba.
Maigidan ya shigo amaryarsa a bayansa ta nade jikinta da wata lafiyayyar lifaya irin ta manya. Duk shigar da za ta yi da gayu ba abin mamaki ba ne domin ko bata auran mai dukiya ita kanta hajiyar kanta ce ga uwar dukiyar da aka mutu aka bar mata da yaranta.
Fuskarta a sake ta zauna kan kujera tana dariya yayin da take kallon Hauwa tana ce wa." Maijego ina fatan ba ki yi fushi da ni ba ko?"
Hauwa ta dan yi murmushi irin wanda babu nisha'di a takaice ta furta." Ban yi ba Hajiya ai maigidan ya ce ba ki ji dad'i ba ya jikin naki?"
Ta ce." Wallahi kam a lokacin na yi ta fama da zazzabi da mura har da ciwon kai, dalilin da ya sanya kenan ban samu zuwa ba."
Ta ce." Allah Ya sawwa'ke abinda ake ta fama dashi kenan."

Na kwanto yaron fuska a sake na mik'a mata shi ta kar'ba da walwala a fuskarta. Ko ba a fad'a ba ita din macace mai masifar son yara ko ba na bata ne wallahi irin rikon da take yi wa Yusi ko ni albarka duk abinda yaranta za su sanya a jikinsu za su ci  babu bambanci wannan kad'ai ya kan sanya ni jin kunya da nauyin yin tutsu akan lamarinta. Kuma sam ba ta da fitina a haka dai tana zaune da kowa lafiya ban ta'ba ganin kishi a idonta ba.
Dad'in ganinmu mun sake muna hira gabad'ayanmu ya sanya shi kashingida kan kujera yana ta murmushi tunda suka shigo bai ce komai ba sai kallonmu yake yi yanayinsa ya nuna ya ji dadin ganin yadda muka fara fahimtar juna.
Sai bayan mun nutsu tukkuna ya gyara zamansa domin mu tattauna tare da samun matsaya akan yadda za mu shirya zama. Legos ne kowacce bata so a cikinmu amma kuma tilas ya kama mu duka saboda babu yadda za a yi ace mu bar shi a can shi kadai alhalin duka muna raye adalci shine a ce a raba.
Ni ya bawa damar magana tunda ni ce gaba dasu gidan cikin nutsuwa na ce." Ni na amince zan dau'ki wattani shida idan ya so ku kuma sai ku raba kowacce wata uku ina ganin hakan zai fi."
Hajiya Maryam tana murmushi cikin nutsuwa ta ce." Anya kuwa ni zan iya akwai abububuwa da yawa da suka sha kaina anan din wallahi ba na so na yi nesa yanzu ko kad'an shi Yallabai din ya sani da za ku yi mini alfarma sai na ce ku barni a nan babu damuwa ta b'angarena in sha Allahu."
Falon shiru ya yi bayan maganarta. Yana zaune bai ce komai ba alamu sun nuna tun a gidanta sun gama maganarsu ya d'aukota ya kawota ne don ya wanke kansa kada mu zarge shi.
Na dubi Hauwa da tun da muke maganar ba ta ce uffan ba na ce." To ke me ki ke ga ni Hauwa."
A takaice ta ce." Duk yadda kuka tsara ya yi mini sister."
Sai na dube shi a nutse na ce." To ka ji abinda kowa ya fad'a menene ra'ayinka?"
"Ra'ayina shine naku giwa, ku tsara yadda kuke ganin za ku zauna babu takura idan kun yi  mata alfarmar da ta nema ni a wajena daidaine amma kada wadda ta kalubalanceni anan gaba.  'Yar uwarku ce ta kuma fito ta gaya

muku dalilanta nasan zamanta anan din cikinku duk kun sani, idan kun goya mata baya to duk 'karuwar ta mu ce bakidaya."
Ban yi mamaki da sunan da ya kira ni ba, domin a wasu lukutan da sunan yake kira na mussaman idan yana so ya rarrashe ni idan mun yi fada ko neman wata buk'ata. Zai ce giwa ko zinariya
Cike da takaicin maganganun da yake yi na ce." To wa ka ji ya ce bai amince ba, na d'auka ai zaman da muka yi gabad'aya don mu samu matsaya ne a junanmu, ni ta b'angarena babu damuwa tunda har na iya d'aukar rabi na basu rabin na ce su raba a tsakaninsu Allah Ya taimake ka duk wannan maganganun ba su taso ba."
Hauwa ta zum'buri baki tana fad'in." To ni ma dai haka na ga ni."
Ita kam dariya ta yi tana fad'in." Na gode sosai, Allah Ya daidaita zamanmu ya kuma amfani zuriyarmu, na gode ni zan koma." Ta mike tsaye tana gyara yafen lifayar da take jikinta.
Na ce." A haba Hajajju ai babu buk'atar godiya duka taimakon kai ne wallahi kada ki damu an zama daya gabad'aya Allah Ya shige mana gaba."
Ta amsa da "Amin." Fuskarta yalwace da fara'a ta kama hanyar fita tana fad'in." Sai na sake zuwa mu gaisa da yarona yanzu bacci yake yi ba mu gaisa sosai ba." Hauwa ta ce." To shikkenan sai an jima.

Tana fita Hauwa ta dube shi kamar za ta fashe ta ce." Gaskiya zan gaya maka irin yadda kake nunawa matar nan kamar itace take auranka ya yi yawa. Ina lefi akan kawaici da karar da muka yi mata har sai ka fad'i wasu maganganu, ai sai ta d'auka hassada muke yi mata, kuma macace mai mutunci da sanin ya kamata gatanan babu wata matsala a tare da ita."

Ya ce." Mai na yi muku kuma, shikkenan daga na fad'i magana sai ku juya mini, halinta na fad'a tana da sau'kin kai gashi dai duk ta girmeku amma bata nuna muku gadarar hakan. Sannan duk da dukiyar da take da ita bata d'auki kanta a wata tsiya ba, ta sake daku sosai ta daukeku 'yan uwa daga fad'in haka sai ya zama lefi."

Na ce." Mu ai dama ba muce maka wata tsiya ba ne, kuma duk abinda take yi ai ba a sanyata ba gani ta yi zata iya, abinda dai zan gaya maka idan zama ya sake hadamu irin wannan muddin kasan zaka goyu da bayan b'angare daya to kawai ka yi shiru da bakinka domin kuwa yin hakan zai janyo maka bacin rai za ka rikita gidanka da kanka."

Don girman Allah kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya ce." Tunda kece Hajja sai ki ba ni umarni kin ji ko, ku abu kad'an mutum zai yi sai ku zarge shi Allah Ya sawwa'ke."
Yana rufe baki Adam da Yusi suka shigo janye da wata madaidaiciyar akwati gaban Hauwa suka ajiye Adam ya ce." Momi ce ta ce wai gashi na Khalil ne."
Ta ce." Ku ce mata na gode sosai Allah Ya kara arziki."

Suka juya za su fita muka had'a ido da Yusi sai yasa dariya ya rike hannun Adam na d'auke kaina ina fad'in." Taka zata kawo ka wurina ne yaro."
Har za su fita sai ya kira su ya dubi Yusi yana fad'in." Mai ka yi mata take harararka?"
A hankali ya ce." Babu komai Baba, ai muna shigowa kullum mu gaisa da ita ko ?" Ya fad'a yana kallon Adam da yake murmushi. Ya amsa da "E Muna zuwa." Ya ce musu ku tafi abinku rigima take nema."
Suka bud'e kofa suka fita kamar wasu 'yan tagwaye komai na jikinsu iri d'aya ne.

Kaya ne na waje irin wad'anda take sayarwa cike da akwati kayan nan kudinsu zai haura dubu dari uku domin duka babu k'ananu har da takalma da tarkace dai kala kala. Tare muka duba kayan yana zaune bai ce mana komai ba, har muka gama dubawa muka rufe akwatin bai tanka ba daga karshe ma sai ya tashi ya haye ya sama ya barmu a falon mu biyu.

To ganin yadda muka k'ulle muka zama tsintsinya madaurinki d'aya ya sanya shi shiga hankalinsa sosai. Tun ranar da muka yi zaman nan bai sake yin wata magana da ta danganci matarsa ba saboda ganin yadda muka nuna masa ba mu yarda ba a tun farkon fari. Dama neman magana ne kawai tunda na farko ai bai ga mun ware ta ba, sannan bai ga muna neman fitina da ita ba, maganace a ka zauna ana tattaunawa wadda kowa yake da hakki akai to babu dalilin da zai sanya shi ya budi baki ya yabe ta a gabanmu bayan alfarmar da muka yi mata. Macace mai nagarta kuma wadda take amfani da ilminta a inda ya dace. Duk irin kushe da kiyayyar da mutum zai yi a kanta wallahi kyawun halinta sai ya sanya wataran mai kushiya akanta ya yaba mata......
Muje zuwa 😃
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN✍*
*76*
Ina jin kunya da nauyinta sosai, ba don komai ba sai don yadda take k'aunar abinda ya jib'anceni. Na jima ban ga mutum mai kara da kawaici irinta ba.

Daf da zamu tafi Legos muka yi waya da Sahura take gaya mini an kawo kudin Yusra an kuma sanya rana shekara daya mai zuwa. Na ce har saurayin ya gama ginin kenan ta ce mini saura kad'an. Daga sanda muka yi waya da ita na ce zan yi magana da garkuwar mata wadda dama tun asali Sahurar ce

ta had'a ni da ita tun lokacin aurana da Alhaji Muntari tun daga sannan da na fahimci magangunta suna da inganci muke zumunci da ita domin daga zarar na bukaci abu zan yi mata waya zata sanya a kawo mini abinda na buk'ata din.
kano take kuma tana aika kayanta kowane gari dole za ta hadawa yarinyar maganin sanyi domin shine abu na farko da ya kamata a fara dashi sannan Yusura bata da cikar kirji sosai har dana gyaransu zan sanya ta had'a mata duka domin kafin zuwan lokacin ta murmure
Na ce da ita idan sun gama magana da ita ni kuma zan tura mata kudin in sha Allahu.
Ta dinga godiya har sai da ta sanya ni na ji haushi na ce ta bari ba na so domin kuwa Yusura haihuwarta kawai ta yi amma na fi ta cin moriya kuma ban yafe mata ba muddin ta sayi ko cokali akan sha'aninta kawai ta bar mini hidimata ta ce. Ta dinga dariya tana fad'in Lallai abin har ya kai haka. Na ce ya wuce hakama a wajena domin kuwa abinda ya shafeni.
Kafin mu tafi sai da na kira Babanmu duka na yi masa bayanin abinda yake faruwa amma ban sanar dashi matsalar da ta kaini wajan Baban Saude ba, sosai ya yi mini addu'a da fatan alheri. Ya kuma tabbatar mini da cewa ana samun cigaba ta bangaran Ummansu Hadiza domin yanzu hankalinta ya fara daidaita ta dawo hayyacinta ta ha'kura da kaddara ta barwa Allah komai. Amma har yanzu Hadiza na can gidan gyaran hali a ajiye ba a kai ga yanke mata hukunci ba ana ta neman ita wadda suka had'a kai suka yi aika-aikar wato Hajiya Alili."
Mun yi waya da anti Yagana na gaya mata za mu wuce legos ban rufe mata komai ba duk na gaya mata irin yadda muka tsara zamantakewar gidan. Ta ce mini hakan da na yi shine daidai a matsayina na babba daga cikinsu dole ni zan dinga 'kokarin d'aukar girma saboda tabbatuwar zaman lafiya.

Sati uku da komawa legos na fara laulaye-laulaye. Ciki fa ya samu abinda ake nema ban gaya masa ba da kansa ya fahimta ya dinga murna kamar me ni dai dariya kawai nake yi masa amma can 'kasan zuciya cike nake da zullumi da fargabar abinda zai kasance bayan na haihu. Shi kuma maganarsa daya Allah Ya sa tagwayene. Kullum abinda yake cewa kenan sai dai kawai na yi murmushi gefe guda kuma na tsananta addu'a akan Allah Ya ba ni d'orarre.
Ban yi tsammanin zai gayawa kowa ba kawai watarana sai Hajja ta kira ni a waya muka gaisa dama kuma sa'i da lokaci takan kira ni, ko kuma ni na kira ta mu gaisa har ta tambayeni zamanmu na ce mata komai lafiya. Cike da farinciki take magana ai maigidan ya gaya mata na samu ciki. Ta dinga ba ni shawarwari akan na kula sosai kada a sake samun matsala irin ta baya. Idan ma ina so sai ta zo ta zauna mini irin na goyon cikin baby Nana aish.
Na ce mata in sha Allahu zan kula sosai amma ta yi zamanta tunda bata da wadataciyyar lafiya bayan haka kuma abun zai zama wani iri muddin Hauwa ta ji labari ba zata ji dad'i ba, abinda haihuwa ba ta farko ba ce, babu wata matsala da za ta faru.

Da wannan na rufe bakinta ta ce mini shikkenan amma dai za ta sanya a rubuce mini al'kur'ani maigirma. Godiya sosai na yi mata muka yi sallama. Hajja macace mai dattako kwarai da gaske tana k'aunata fiye da tunanina don ma an yi yun'kurin shiga tsakanina da ita a baya.

***

Watanni shida ciki ya bayyana ya fito sosai duk wasu gwaje-gwaje da scanning an yi mini tagwayene duk mata. Ya rasa ina zai sanya rayuwarsa duk fitina irin tasa ha'kura ya yi a sati bai fi ya kwanta da ni sau biyu ba wai kada yaran dake cikina suga kamar an takura musu. Acewarsa yawan motsa ni da yake yi zai sanya su dinga shan wahala. Abin sai ya ba ni dariya da mamaki. Tun suna ciki basu fito ba yana nuna musu k'auna irin haka, ai ni ma 'yar wani ce mai yasa bai duba hakan ba, a lokacin da ban samu cikin ba yake galabaitar da ni, wato kenan kowa nasa ya sani.
A haka na yi wata shida a tare dashi a legos  babu wanda bai san ina da ciki ba domin kuwa duk ya sanar da iyalinsa Hauwa har bidiyon call muke yi da ita musha hira Khalil ya yi wayo sosai yana koyar zama. Wasu lukutan ma idan na tambayeta yana Ina sai ta ce yana can wajansu Yusi idan ba nono ya buk'ata ba a can yake yini idan ba makaranta. Idan kuma da akwai idan za su tafi sai su mayar mata dashi. Da kanta ba tambayarta na yi ba take gaya mini yadda suke zaune lafiya domin a wasu lukutan ma takan shiga wajanta su hira itama kuma takan shigo. Na ji dadin hakan sosai da sosai, yanzu dai hankalinmu ya kwanta babu wani kishi na jahilici bayan haka kuma dukanninmu ba yara ba ne iyaye ne masu yi wa na kasa dasu nasiha.

Tare muka koma da shi abujan sai da ya yi sati biyu tukkuna suka juya shi da Hauwa da yaronta. Duk dauriyar da ya dinga nunawa sai da na gane hankalinsa gabad'aya yana kan abinda yake cikina kawai don ba yadda zai yi ne ya dawo da ni, ya d'auki Hauwa domin babu irin rarrashin da bai yi mini ba akan na zauna na haihu a can a gabansa a cewarsa sai hankalinsa ya fi kwanciya na ce masa a a, mun riga ai mun gama magana tuntuni babu dalilin da zai sanya yanzu a warware idan har za a yi mini adalci a lamarin wattani uku kacal za su yi a can shi da ita ta dawo a lokacin ma na haihu in sha Allahu rabbi ko da ban haihu ba to kad'an ya rage. Da haka ya ha'kura smma ba don ransa ya so ba.

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Bikin Hamusu ne ya tashi gadan-gadan domin kuwa yarinyar da ya jima yana nema burin mahafinta ya cika ta kammala karatunta wannan dalilin ya sanya uban ya ce a d'auki wata biyu kacal a yi a gama komai
Ya kira ni yana gaya mini  duk abinda yake faruwa. Na ce masa duk abinda yake bukata ya nemi Usaini domin shi yake kula mini da shagunana ya had'a lefe abinda babu ya fitar da kudi ya saya amma ya yi mata akwatina shida ya kuma sanya mata kaya masu quality. Godiya ya dinga yi mini sosai na ce

babu buk'atar hakan domin kuwa duk abinda na yi masa babu fad'uwa hakkinsa ne tunda dukiyar tare muke nema. Gini kuwa dama ya kammala abinsa can unguwar maidile ya sayi fili ya gina irin na zamani tuntuni gidan ya kammalu har bidiyo ya yi ya turo mini. Na ce masa idan sun tare ya nemi solar mai girma ya saya sai a sanya masa a gidan tunda na lura unguwar kamar sabuwa ce bata gama cika ba babu wutar nepa.

***

Bikin ya matso sosai daga can suna ta shirye-shiryen a lokacin cikina watanshi bakwai da satika. Da kyar nake gudanar da abubuwan da suka zame mini dole saboda nauyin da cikin ya yi mini ya yi girma sosai ya kara sanya ni na d'unkule. Amma ina da burin so na ga na samu halartar bikin Hamusu dalili kuwa anan shine yaron ya wuce komai a wurina ni ce uwa kuma uwar dakinsa.
Daga tambayarsa akan ya barni na je tunda ai tafiyar jirgi ce ba mota ba kuma zan motsa jikina na shiga cikin jama'a. Sai abin ya zama rigima saboda ya san ma ba bari na zai yi ba ya mayar da abin tashin hankali ya dinga sakin maganganu har sai da ya fusata ni dama haka yake so na ji haushi mu yi fad'a na kashe wayar raina a b'ace cikin zuciyata Ina fad'in idan ba zaka bari na je ba menene kuma na yin tijara kawai a ce ba zan je ba shikkenan sai magana ta mutu.

Haka aka ci aka cinye bikin Hamusu babu ni uwar biki, sai hotona da ya turo mini nan naga ashe har da su Dada da anti Yagana sun samu damar zuwa bikin. Na ji takaici sosai amma haka nan na ha'kura na yi masa addu'ar samu zaman lafiya madawwami. Amma na yi masa alkawari idan na haihu lafiya takanas zan zayarci kano saboda shi.

***

Duk abinda Ubangiji Allah Ya hukunta walau mai dad'i ko mara dad'i yana da iyaka. Kuma cikar mumini kenan yarda da kaddara kowace iri ce wannan shine yake tabbatar da cewa Allah yana sane dakai kuma duk jarabtar da ya yi maka idan ka cinye ba ba tare da ka bi wata hanyar ka sa'ba masa ba to zai maka tagomashin wanda kai kanka ba ka yi tsammanin irinsa ba.

Haihuwa na yi cikin koshin lafiya haihuwar da ta sake bud'e kofofin arziki da alherai masu yawa. Duk irin zullumi da fargabar da na kasance a ciki a lokacin da nake d'auke da cikin da haihuwar ta zo sai na yi cikin sauki da taimakon Allan da ya ba ni ajiyarsu a cikin cikina. Lafiyata lau hakan nan yaran ma da na haifa lafiyarsu lau duka ba su d'auke da kowace irin lalura daidai da irin murar nan da ake haifar jarirai da ita tagwayena ba su d'auke da ita. Tagwaitaka kuwa gadonta na yi tunda Babanmu ya yi bibbiyu sau biyu ba abin mamaki ba ne.
Tubarkala ma sha Allah shine abinda kowa yake fad'a a kansu domin kuwa yadda Allah ya gina musu jiki da lafiya tun a ciki ba wanda zai d'auka cewa 'yan tagwayene dalili wasu akan haifesu da rashin lafiya irin ta jarirai ko

yan'kwanewa da yamushewar fata, su kam  kalau suka fito cikin mahaifa daya kamar kuma an tsaga kara babu ita inda suka yi bambanci. Tunda aka haifesu ake ta hasashen da wa suke kama wasu suce da ni, wasu kuma su ce da babansu. Ita Hajja ma cewa ta yi da inna Uwani suke kama mai gabad'aya kenan. Jin haka ya sanya ina Uwani kasa rufe bakinta daga zarar an yi magana sai ta ce ai da ita suke kama. Can dangin Hajja suka kwaso domin ni kaina basa kama da ni balle kuma Babansu Hajja ta ce suna kama da inna Uwani shi kuma ya ce da Samira suke kama matarsa ta farko. Ni dai dariya kawai nake yi musu domin ba ni da ta cewa ganin yaran daidai da yatsuna ba su d'auko ba.
Umara ya tafi a tsakankanin haihuwar ya je ya nuna godiyarsa ga Allah subahanawu-wata'ala. Satinsa daya ya dawo ya ce zai shirya walima domin sake nuna godiyarsa ga kyautar da Allah ya yi masa. Ban so ba saboda ba na so abinda zai kawo rud'ani a zamanmu na ce masa lokacin da aka yi masa haihuwar fari ma bai  yi ba sai yanzu ya kamata ya bar shi kawai umarar ma da ya yi ta isa. Fad'in haka ashe lefine a wurinsa yana fad'a na kyaleshi ya yi yadda yake so kudinsa ne kuma yaransa ne ba zan tsara masa abinda zai yi ba, Yana da kyau ya nunawa Ubangiji godiyarsa ta sigogi da yawa tunda Allah Ya yassare masa to babu ruwana idone nawa.....
Humm
Mu je zuwa dai. Tsugonan ta kare ko bata 'kare.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip  1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*
*77*
Rabuwa na yi dashi kawai na daina mayar masa da martani ganin iyayensa Hajja da inna Uwani a gidan, kuma daidai gwargwado suna nuna mini kulawa da kara tare da yin tiriri da yaran mussaman inna Uwani da motsi kad'an idan ana maganar kammanin yaran take amshewa tare da tabbatar da cewa da ita suke yin kama. Dukkaninsu daga ita har Hauwan na kasa fahimtar menene a can kasan zuciyarsu domin duk yadda na kai ga so lallai sai na hango cewa abinda suke yi mini ba don Allah ba ne na kasa sun 'boye sosai kuma ko da da wani kulli a ransu ba su nuna ba, amma zahiri Hauwa ta yi kyan kai da ta iya jimirin kawar da kanta daga jin haushin d'igimin da ya d'auka adalalin samuwar yaran, don gabad'aya tunda aka yi haihuwar ya rasa sukuni haka zalika mu ma haka don motsi kad'an za a yi zai ce ba a yi masa daidai ba ko kuma wata daga ciki ta yi kuka ko yana sama idan ya ji sai ya sauko Yana tambayar dalili har kunya da nauyi nake ji wani lokacin domin inna Uwani ce take dauwaniya da su Hajja tana dan taimaka mata kadan.

Gefe guda kuma Hauwa na hidimar d'orawa da saukewa yini take yi a kicin saboda ba mu da mai aiki mace sai maza, na dai kudire a raina duk lokacin da na je kano to kafata kafar baba Tabawa
Sannan ni kaina Hauwa  hidima take yi mini ta fannin abinci ga maigidan da tsofffin iyayenta. Lokacin da ya dinga fad'a akan me zan hana shi yin abinda yake so sai da iyayensa suka ji 'kananun maganganun da yake yi sai nema yake yi ya mayar da abin rigima da na gaji kawai sai na rushe da kukan b'akinciki ya ina cikin d'aita da rintsin haihuwa a sanya ni a gaba da tijara, kawai saboda na ce kada a yi walima shine lefi da fad'in bakaken maganganu.

Hajja da inna Uwani  suka shiga maganar. Akan na rabu dashi ya yi ai abin alheri ne a tara mutane a ciyar dasu a kuma yi addu'a, dama walima aka sani a tsarin addinin musulunci ba wani abin ba ne. Ganin yadda ya samu goyan bayansu akan hakan ya sanya ban sake wata magana ba, sai da muka yi kwana biyu ba mu yi magana ba sannan muka shirya don shine ma ya dinga neman shirin ganin da mutane a gidan na kula shi domin kada suga kamar ina da mugun hali. Amma ba wani ya'ke masa baki nake yi ba don mugun haushinsa nake ji akan abinda ya yi mini.

Amaryarsa  Momi akwati biyu ta yi da kaya kowacce shake wai Hassana daya usaina ma d'aya. Wallahi rasa bakin magana na yi a lokacin da na bude kayan ina dubawa. Da yake duk a gabansu ne Hauwa har tana cewa kada matar nan ta rusa jarinta akan yi wa 'ya'yan miji gwaninta. Ina dariya na ce ko daya tunda ki ka ga tana irin wannan kyautar ta yi nisa ne wata'kila yadda kike d'aukarta ta wuce haka. Hajja ta ce kuma ma dai mai son yi ce domin wasu  akan su bayar sun gwammace wuta ta cinye domin Ubangiji yana duba duk wanda ya azurta baya fitar da kazantar dake cikin dukiyarsa da kansa zai fita ta hanyar tashin gobara ko ta wata sigar ta daban. Ta nisa kafin ta cigaba da cewa mijinku shi yake gaya mini cewa har gidan marayu ne da ita a can garinsu jos din tana d'aukar nauyinsu bayan makarantu da massalatai da ta gina duka hobbsi ga tsohon mijinta da ya rasu. Wannan dalilin ya sanya ni jin kaunarta a cikin raina domin kuwa macace ta gari, ina kara horarku ku zauna lafiya da ita, kuma kada ku dauketa a matsayin kishi sai yayarku domin ta girmeku ku muntata da kyau.
Sosai jikina ya kara yin sanyi da sha'anin matar wato mutane suna daukarwar kansu zunubi a duk lokacin da suke munana zato akan mutum alhalin ba su da sheda kawai zargi suke yi da k'age. Sai na tuna irin maganganun da Sahura ta dinga fad'i a kanta a lokacin auransu da maigidan ya zama dole kuwa Sahura ta yi nemi gafarar Allah domin kuwa ta yanke hukunci akan abinda ba ta ta'ba ga ni ba.

To walima ta kyau sosai, kuma ta samu halartar manyar mutane malamai da ma'aikatan gwamnati har ma da 'yan siyasa. Sahura ta samu zuwa itama yan gidanmu kuwa Babanmu ya samu halarta tare da Baba Sule sai anti Sakina da Fati. Anti Yagana da Yafalmata sun zo Baban Saude kuma a lokacin baya

gari sai da ya kira ni a waya ya yi mini barka ya kuma kira maigidan shima ya yi masa barka. Hamusu ma ba a bar shi a baya ba ya zo shi kadai Amma domin da ya gaya mini za su zo tare da Gwaggo na ce masa a a saboda tafiyar mota ce Kuma bata da lafiya sosai na yi alkawarin idan na yi arba'in da kaina zan kai mata yaran ta sanya musu albarka.

An yi hidima sosai  yara sun samu alheri irin wanda ba zai misaltuba hotonsu kuwa yana ta yawo a kafafen sadarwa tare da yayansu Khalil da ya yi wayo har yana gudu da kafafunshi.

A daran ranar gajiya ta kayar da ni, ana yin sallar magriba da kad'an baccin gajiya ya kwashe ni. Maganarsa ce ta tashe ni na bude ido Ina kallonsa yana tsaye sai kuma ya zauna a gefana na tashi zaune ina d'an hade jikina tare da d'an matsawa. A tak'aice na ce." Ina yini." Ya amsa cikin kulawa yana ta kallona har na tsargu. Na ce." Wani abu ne ya faru?"
Ya girgiza kansa a tsanake ya furta." Na gode mini giwar gidana."
Murmushi na yi wanda babu nisha'di a cikinsa na ce." Godiyar ta mecece?"
Ya fito da wayarsa hotonan yaran yake kallo yana murmushi kafin ya nuna mini na kalla ban ce komai ba. Sai na ji ya ce." Kin biya ni Amina, na kuma yafe miki abinda ki ka yi mini abaya." Ya nisa kafin fuskarsa ta sake yalwata da annashuwa ya furta." Da ki ka tashi ba ni yara sai ki ka ba ni biyu kuma masu kama da Samira Amina na gode, na gode wallahi idan na kalli yaran nan ina jin wani irin farinciki mara misaltuwa."

Don Allah kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Sosai na iya danne tsaki da harshe da gand'ar bakina ke ko'karin furzarawa. Na ce." Na farko dai ba ni za ka yi wa godiya ba Allah za ka godewa domin shine ya baka ba Amina ba. To ai yanzu ka fadi dalilin  da ya sanya ka dimaucewa akan yaran bawai a karan kanka ba ne, a a saboda suna kama da wata can daban. Hakan bai dame ni ba dama hausawa sun ce kyan d'a ya gaji ubansa, ka daina gode mini ka godewa Allah ko ka je ka tashi Samiran daga kabarinta ka ce kana yi mata godiya dalili yaranka sun yi kama da ita."
Tunda na fara maganar ban tsahirta ba sai da na dire  tukkuna tsakin da nake ta dankwafewa sai da na furzar dashi domin idan bai fita ba akwai matsala, na koma na kwanta abina.
Ya jima yana kallona da yanayi na mamaki da takaici kafin ya ce.'' Yanzu ina Samiran take Amina?"
Na ce." Oho!
Sai ya gyad'a kansa ya tashi yana fad'in." Ni ba zan yi rigima dake ba domin na gane so kike ki tsinka ni a cikin mutane don haka ki huta lafiya." Ya juya da niyyar fita. Na kuwa bi bayansa da harara ban so ya kyale ni ba a lokacin na so ya tanka na amayar da b'acin ran da ya guma mini ahe da biyu yake ta abubuwa akan yaran saboda suna kama da inna Uwani da kuma 'yarta.

Hawaye suka zubo mini na haifi yaran na ci wuya kuwa ta laulayi da zafin haihuwa amma ko yatsuna babu wadda ta d'auko Allah na tuba ka yafe mini.

Gida ya watse ya rage mu kad'ai. Ni da Hauwa muka cigaba da rainon yaran a wasu lukutan kuma Hajiya Maryam tana aikowa a d'aukar mata su, har su d'an jima a wajenta kafin su dawo.
Kwanana arba'in da takwas na shirya zuwa kano. Amma ina jimanta yadda zan yi dawaniyar yaran ni kadai dama burina idan na isa na samu Baba Tabawa mu yi magana idan ta amince mu tafi tare domin zamanta a tare da ni zai taimaka kwarai tunda kaf gidajensa daga na Legos din har na abujan babu mai aiki mace duk maza ne. Hajiya Maryam ce kawai naga tana da masu aiki dattijuwa mai suna Taburni Mairo kuma itace  take yin dawaniya da yaran idan an akaisu can wajenta.
Ya ce Hauwa ta shirya sai mu tafi tare. Sosai na ji dadin hakan kuwa ban yi nauyin baki ba na yi masa godiya sosai ya ce  kwana hud'u kawai ya ba mu dama za mu yi mu dawo. Kwanakin sun yi kadan amma ban iya gaya masa ba saboda Ina gudun ya ce ya fasa ma gabad'aya tunda har yanzu yana jin haushin abinda na yi masa sharewa kawai ya yi saboda yasan idan ya ce zai rama sai mun yi dan karamin ya'ki a gidan. Ni kuma fahimtar a kusa yake ya sanya nake ta lallabawa kada ya ce ba zan je ba.

***
Alhamdulillahi lafiya lau muka sauka a kano. Gidana na sharad'a muka sauka inda muka iske shi tsaf Baba Tabawa da Yusura sun gyara ko'ina har an yi mana abinci. Na yi mamaki kwarai da gaske  nasan wannan aikin ba na kowa ba ne sai Sahura domin mun yi waya da ita ana i gobe tafiyar har ta na yi mini tambayoyi ashe abinda ta shirya kenan. Hidimar tace yin cefane mai kyau ta kuma sanya a yi mana abinci mai rai da lafiya. Cikin zuciyata na sake kud'ire wani alheri da ya jima a cikin zuciyata.
Da daddare Ayuba ya shigo mana da kayan abinci ya kai a store bisa umarnin maigidan ne ya tsaya muka gaisa sosai kafin ya juya ya fita.
Ko da na gayawa Baba Tabawa kudirina ba ta yi jayayya ba ta ce ta amince za ta bi ni duk inda zan je, yadda na nuna mata tausayi da kulawa a lokacin da take neman d'auki yanzu ne daidai lokacin da za ta biya ni. Ina dariya na ce mata ai ni don Allah na yi mata ba don ta biya ni ba. Daga ranar kuwa ta shiga hidima da yaran bakid'aya.
To duk inda ya kamata na je a tsakankanin kwanakin da ya ba ni mun je ne tare da Hauwa domin duk inda na ajiye kafata itama nan take ajiye tata. Baba Tabawa na goye da Hassana ni ina goye da Usaina ita kuma Hauwa tana ri'ke da Khalil a hannunta.
Ayuba ne ke jan mu a mota rana ta farko a gidan Gwaggo na yini sai yamma muka yi mata sallama muka nufi gidanmu anan muka yi magariba. Sannan muka nufi gidansu Sahura dake kusa damu muka gaisa sosai da mamansu ta d'auki yara ta sanya musu albarka.

Washe gari a gidan Hamusu muka yini amarya ta zama 'yar gari Hamusu kuwa ya rasa Ina zai tsoma ransa ya kai ya kawo ya siyo wannan ya ajiiye ya siyo wannan ya ajiiye bayan uban girkin da ya sanya aka yi mana. Sai da na ga abin ya yi yawa tukkuna na yi masa magana sannan fa ya dan samu nutsuwa.
Dubu ashirin na bawa amaryarsa na ce ta sayi janbaki ta kar'ba tana godiya ta rako mu har bakin gate.
Da muka fito tare da shi nake tambayarsa ya ake ciki da karatun Turmizi tunda shine ya shige gaba wajan kai shi makaranta kamar yadda maigidanmu ya yi alkawari nan yake ba ni tabbacin alhamdulillahi an samu cigaba kwarai da gaske domin hankalin yaron ya fara dawowa jikinsa domin lokacin da aka kai shi makarantar ma baya hayyacinsa dalilin irin shaye shayen da ya fara yi ya hadu da wad'anda suka fi shi wayo suka bashi kwayoyi har hankalinsa ya gushe garkuwar jikinsa ta raunana. A Tasha aka je aka d'auko shi yana zagari da kai kawo tare da sururai. Ya ce ko wancan watan da ya je dubasu ya same shi garau kuma ya kama karatu ka'in da na'in domin malaman a tsaye suke a kansa kuma makarantar cike take da tsaro babu ta inda yaro zai haura ya gudu.
Kamalu kuwa farkon watan da zamu shiga zasu sallameshi da izinin Allah dama kuma shi mun gama magana dashi zai zauna a hannunsa domin taimaka masa da cigaba da gudanar da harkokin da muke yi na kasuwanci.

Rana ta uku kuwa da wuri muka fita saboda gida biyu nake so mu je, gidan Sahura da gidan Alhaji Muntari can muka fara zuwa saboda nasan idan gidan Sahura muka je da farko bai zama lallai ta bari mu fito da wuri ba.
Alhamdulillahi na ji dadin ganin yadda anti Maimuna ta samu nutsuwa ta kafa sana'a kala uku tana sayar da itace manyan d'auri sannan ga buhuhunan gawayi anan a jibge kusa da itacen sai manja da man kulli da take sayarwa galan-galan. Lokacin da muke je duka yaran suna makaranta tunda da safe ne. Na tambayeta Salima ta ce itama ta samu koyarwa a wata nursery dake bakin titi gaskiya ne a lokacin da Babansu yake raye ya yi kokarin sanya su a makaranta da wannan yarinyar ta tsira gashi har wasu suna amfana da iliminta kuma tana samun kwabo da dari.
Na tambayeta Jamila ta ce mini ta ji dai kwanaki an ce ta yi aure amma kuma tana zaune aka zo aka gaya mata wai an ganta a wani hausa film da ta yi bincike sai ta tabbatar da itace din auran ne ya mutu ta shiga wasan hausa.
Sai abin ya ba ni dariya da mamaki cikin zuciyata na ce to Allah Ya kyauta.

**
Yini zur muka yi a gidan Sahura ta dinga yi mana soye-soye har da su wainar fulawa. Ta soya mama dubalan cikin bokiti wai mu tafi dashi. Da daddare kuma ta hana mu tafiya sai da gama awara nan ma ta cika mana fulas wai idan muje gida sai mu ci a madadin abincin dare. Sahura kenan sarakan kirki da kyauta......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN□*
*78*
Washe gari ranar da za mu tafi kenan da wuri ya yi waya ya ce sha biyu ta yi mana a filin jirgi domin ya gama yi ma shiri, dama na gaya masa tare muke da Baba Tabawa ya ce babu damuwa, don haka da wurwuri muka shirya na ce Ayuba ya kai ni gidan Baba Sule domin shi kad'ai ne ban je na gaishe ba, ita kanta Hadiza na so na kai mata ziyara amma lokaci bai ba da damar hakan ba, sai da na bawa Ummansu kudi na ce a yi mata siyayya a kai mata.
A gurguje muka gaisa da Baba Sule da iyalinsa na yi musu alheri daidai Gwaggwo sannan muka nufi gidan Hajja wanda daga can din sai kuma mu wuce airport.
Hajja bakinta kamar gonar audiga ganinmu a tare kanmu a had'e sannan ga 'yan jikokinta da take ta burin Allah ya nuna mata su.
Ita kyautarta dama ta turarece domin idan ta je saudiya su take sayowa da dayawa duk wanda ya ziyarceta ta bashi, ta had'o mana da yawa na jiki dana wuta tana ta yi mana addu'a da fatan alheri cikin tsananin farinciki mara misaltuwa.

Ganin da sauran lokaci da muka fito daga gidan Hajja na ce da Hauwa mu je gidan Hajiya Saratu don ni sai na ce zuwana gidanta d'aya tunda nake tunda bata fiye sabga ba yaranta duka biyu maza ne kuma babban yana can Egypt yana aiki da matarsa da yaransa. Mai bin sa kuma yana chana yana aikin koyarwa a wata makaranta, da yake wanda take aure dan boko ne sosai.
Shiru ta yi mini ba ta ce komai ba yanayinta ya nuna dai kamar ba ta son zuwa. Nan na fahimci cewa har yanzu akwai rashin jituwa a tsakaninsu tun daga lokacin da suka samu sa'bani akaina basu daidaita ba. Zaman  amana muke yi a yanzu dole a tsakaninmu duk wanda ya hangi kuskure daga b'angaran d'an uwansa idan har da amana bai kyautu ace ya yi shiru ba mussaman idan aka yi duba da cewa ta dalilina suka samu matsala gashi zumunci ne mai karfi a tsakaninsu.
Tun kafin mu shiga mota na nuna mata fa yana da kyau ta gyara domin kuwa kaf Hajiya Saratu ba'asar yin ta ba ce, ta wuce matsayin Yaya a wurinta sai dai uwa, gashi kuma yayar mijinta ce dole ita za ta yi hakuri ta nemi hanyar daidato domin su gyara zumuncinsu tun kafin yaranta su fahimci halin da ake ciki.
Jikinta ya mutu sosai a lokacin da nake yi mata maganar ba kuma ta yi mini jayayya ba ta ce mu je din, dama ai ita bata d'auka da zafi ba, ita Hajiya Saratun ce ta ga kamar har yanzu bata huce ba domin koda ta haifi Khalil ba

ta je mata barka ba. Na ce mata kada ta duba wannan kawai ta yi 'ko'karin gyara kuskuran da ta yi a baya.
Takuwa ji dad'i sosai da muka je gidan nata, kuma duk yadda Hauwa take d'ari-d'ari da ita sai ba ta nuna mata komai ba a fuska ba, ta sakar mata fuska kamar babu wani abu da ya ta'ba faruwa na saba'ni a tsakaninsu. Sosai na ji dad'in ganin yadda suka samu daidaito da fahimtar juna. Muka rabu cikin girma da mutunta juna ta yi mana alheri sosai tunda dama can a sanin da na yi mata itama hannunta a bud'e yake.

***
Bayan komawarmu da kwanaki uku na kira Hamusu a waya na ce masa ya fitar da kudi ya kuma nemi kwararrun ma'aikatan da za su gyara gidana na kuntau sannan ya sayi set din kayan d'aki da kujeru da gado labuleye masu kyau ya sanya a shirya gidan. Idan komai ya kammala kawai ya kaiwa Sahura mukkulin na mallaka mata shi gabad'aya tunda dama takardun suna hannunsa sai ya bata. Shi kansa ya taya ta murna sosai ya kuma bani tabbacin zai kammala komai a cikin sati d'aya.

To mun yanke shawara har da maigidan kan cewa tare za su sake komawa da Hauwa saboda yanayin garin koyaushe cikin ruwa ake yi duk da gidansa ya sha bam-bam da sauran gidajen da suke garin legos amma dai hankalinsa ya fi kwanciya da mu zauna anan abuja zuwa wattani shida lokacin yaran sun yi k'wari sosai..
Na ji dadin hakan sosai kuma na yaba da yadda suke nuna mini kulawa dashi da matarsa. Sai dai tunda muka yanke wannan shawarar nake cin 'kaniyata a hannunsa duk ranar girkina nakan ji jiki kwarai da gaske baya daga mini 'kafa, idan na yi magana sai ya ce abinda ma ya kusa tafiya. Haka na yi ta hakuri dai har ya kammala musu shiri suka tafi sannan na samu sa'ida.

**
Cike da mamaki Sahura ta kira ni a waya tana tambayata wai Hamusu ya kai mata mukulli da takardun gida in ji ni, na ce mata 'kwarai kuwa gidana na kuntau na mallaka mata halak malak. Sai ta rasa bakin magana ta yi shiru ta kasa cewa komai ba. Sai da na sake yin magana tukkuna na ji sautin muryarta cikin rawa kamar za ta yi kuka tana yi mini godiya na ce kin wuce haka a wurina Sahura dukiyata taki ce kuma ki shirya zuwa umara in sha Allahu farkon Azimi maigidan ya baku kyautar kujera ke da Anti Yagana da Baba Sule.
Sai ta fashe da kukan da take ta b'oyewa na kashe wayar ina dariya da mamakin kukan da take yi a ganina ai Sahura ta wuce duk wannan abin a wajena yadda nake jinta a raina kamar anti Yagana da muka fito ciki d'aya.

Gudun aure littafine na kudi ki ji tsoron Allah ki biya ni hakkina kafin ki karanta

***

Ubangijina ya jarabce ni da abubuwa da yawa a lukutan baya wanda har nake ganin kamar ni kadai ce nake  cikin masifa da ibtila'in rayuwa. Na yi kuka kamar ruwan idona zai tsiyaye yadda na ji dad'i na kuma godewa Allah shine ban ta'ba had'a Allah da waninsa ba, shi kadai na k'adaita na kai kukuna wurinsa domin kuwa nasan shine mai iko da kowa.

Allah na gode maka wannan kalmar ba zata ta'ba yankewa daga bakina ba har na koma ga mahallicina. Yadda Allah Ya kar'bi adduata a yau da Kamalu yake zaune a gabana cikin Kamala da suttura tare da tsantsar nutsuwa da wadataccen ilimin Islama a tattare da shi. Kamalu ya girma ya zama saurayi mai tattare da tsafta nutsuwa da ladabi. Ban iya daurewa ba rungumeshi na yi sosai a jikina ina kuka ina tuna mahaifinsu har shi ma ya kasa daurewa ya fara taya ni Baba Tabawa dake goye da Hassana a bayanta ta fito daga kicin da saurin domin sautin kukan namu har can ta tsaya tana ba ni baki wai na daina yin kuka Allah ya kamata na godewa domin duk abinda yake faruwa hukuncinsa ne. Da kyar na yi shiru shi ma ya rike hannuna gam ya kasa saki.

Cikin wannan halin Yusi da Adam suka shigo domin lokacin da aka kawo mini Kamalun ba sa nan. Wani tsalle Yusi ya yi ya rungumeshi   suka fadi a wajan Adam ya dinga yi musu dariya. Shi ma Kamalun dariya yake yi wa Yusi ganin yadda duk kwalla ta cika kwarmin idonsa.

Ya dube ni yana tambayata wai wane irin abinci Yusi yake ci ya kumbura irin haka, ko bashi da lafiya ne. Na ce masa lafiyarsa lau hutu ya samu da jin dadi. Adam dai yana tsaye yana ta dariya da yake yaro ne mai sakakkiyar fuska kamar ta Mamansa. Kamalu ya gyara hannun rigarsa ya daga k'wajinsa na hannun dama duk a mur'de ya dubi Yusi yana  cewa ka ga ni da nake cikin hatsi ina kuma aikin gona da motsa jikina dubi kwanjina malam haka ake son namiji ya kasance.

Adam ya ce abinda ake gaya masa kenan amma kullum sai ya ci nama ya zuba suga da madara da vombita da yawa ya tea Momi na bashi goyan baya. Yana dariya yake cewa ku raka ni na je na gaishe da Momi ni ma." Ya mike tsaye ya shiga tsakiyarsu suka kama hanyar fita. Ni da Baba Tabawa muka bi su da kallo cike da wani irin farinciki a zukatanmu bakid'aya.

Abin mamaki da d'aure kai. Tun ina tsammanin dawowar Kamalu har na cire rai domin kuwa sha daya na dare har ta gota. Zuciyata ta shiga yi mini nazari ko kallo suka yi ne, ko kuma dai yaran sun d'auke masa hankali sam ban kawo cewa matar gidan ce ta hana shi dawowa ba sai da na kira ta a waya na tambayeta tukkuna kai tsaye ta ce mini zai kwana cikin 'yan uwansa ne. Mamaki mai yawa ya lullube ni amma ban iya cewa da ita komai ba muka yi sallama har tana cewa a shafa mata kan twins.

Da zullumin lamarin na kwana a cikin raina. Don haka gari yana wayewa ban yi kasa a gwiwa ba na kira maigidan a waya da muka gaisa na gaya masa fa makaranta sun sallamo Kamalu yanzu haka muna tare da shi anan abuja jiya Ayuba ya kawo mini shi. Sai ya ce ai Hamusu ya kira shi a waya ta gaya masa. Daga can makarantar ma sun sanar da shi. Na ce zai yi sati sati daya

anan domin mun gama yanke magana da Hamusu zai zauna a can wurinsa domin dora shi akan harkokin da muke yi.
Bud'ar bakinsa sai ya ce bai amince ba dama ai tuntuni ya gaya mini idan yaron ya dawo zai had'ashi da d'an uwansa su tashi tare . Idan kuma ina ganin hukuncin da ya yanke bai yi mini ba sai na yanke nawa tunda duka 'ya'yana ne.
Na dinga kokarin nusar da shi hakkin da dangin ubansu suke da shi akan yaran, idan fa magana za a yi ta gaskiya yana da kyau a ce suma an basu damar yin  abinda suke so da yaran. Ya fahimci dalilina amma sai ya mayar da abin rigima . Ganin haka ya sanya na kashe wayar raina a b'ace.
Ni wannan 'karfa-'karfa da ake yi mini akan yarana ya fara isata wallahi duk na gane take-takensa shi da matarsa wata'kila ya yi mata kyautar yaron tuntuni ban sani ba, tunda haka ya bata Yusi ba tare da neman izinina ba.
Wannan lamari ya janyo mana sa'insa sosai a tsakaninmu, wanda har sai da na gaza ha'kuri ina kuka na kira Hajja na gaya mata ta yi masa magana ta ba ni ha'kuri sosai ta ce za ta sanya a kira mata shi a waya.
Ranar kuwa da suka yi waya Baban Saude ya kira ni tare da rufe ni da fad'a irin wanda ban ta'ba tsammani ba. Shiru kawai na yi Ina sauraransa wato tunda na kira mahaifiyarsa to shi ma bari ya had'a ni da nawa iyayen. Baban Saude ya gama nasa fadan. Anti Yagana ma ta kira ni tana yin nata tana ce wa ba ni da wato har yanzu kuma har yanzu na kasa gane irin k'aunar da mijina yake yi. Idan duk zai d'auki yaran da zan haifa ya bawa matarsa ai ta cancanta ne tunda kowa ya shaida ita din uwar marayu ce. Har da Allah Ya isa ta yi mini idan na kuma tashin maganar da kanta zataje ta yi wa Gwaggo bayani tana da tabbacin samun goyon baya da amincewa daga wurinta.
Kuka na ci na 'koshi na ha'kura na kyalesu kullum dai da safe suna shigowa mu gaisa. Shi ma kuma kamalun ya fi sakewa a can saboda yaran don ma shi Salim yana can saudiya yana 'dora karatunsa sai  'yan yaran Nusaiba Sahib da Yasmin da ake kawo su duk ranakun weakened.

Kiran Hamusun na yi a waya na yi mass bayani duk yadda al'amirin ya juye. Sai ya dinga dariya cike da nuna rashin damuwarsa yake ce mini wannan ai ba wani abu ba ne hakan ma da aka yi daidai ne da kuma hujja mai k'arfi.
Dole na ha'kura na zubawa sauratar Allah Ido, amma kuma ban ta'ba nunawa matar wani abu a fuska ba, dalili ta wuce na ya'keta akan komai ba, wanda ya riga ya ce yana son naka ai kai yake k'auna.....

Tofa wata sabuwa 😳
Shin wai mai Hajiya Maryam take nufi ne, alheri ne ko kuma sharri Allah ne kadai yasan abinda yake cikin zu'kantan bayinsa.....✍
Muje dai zuwa.
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita

ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*79*
'Kwarai na danne hakan a cikin raina domin duk 'kwa'kwata na kasa gane abinda yake cikin zuciyarta dalili koyaushe alherinta a gare ni ru'banya yake yi.  Ni dai kawai na zama kamar mutum mutumi tare da zubawa sarautar Allah ido, ita da mijinta suka yi duk yadda za su yi wurin mayar dashi makaranta domin ya samu shedar kammala secondary tunda wannan da ya gama sun fi karfi akan al'kur'ani da sauran littafan addini. Ban ce musu komai tunda bai sanya ni a ciki ba kawai dai na yi masa shiru har sai da yaron ya fara zuwa makarantar  tukkuna watarana da daddare yake sanar da ni a takaice na ce ." Allah Ya taimaka." Daga haka ban sake magana ba. Na gyara kwanciyata ina lumshe ido.
Na ji maganarsa yana cewa." Tashi zaune ina so na yi magana dake."
Na tashi kamar yadda ya buk'ata din ban ce komai illa Ido dana zuba masa."
Ya sassauta sosai kafin ya furta." Kina ganin kamar ba a kyauta miki ba ko Amina."
Na ce." Da aka yi me?"
Ya nisa kafin a hankali ya furta." Kin san akan abinda nake magana ai."
Sai na gyada kaina a tsanake na ce." Ai kai ma kasan ba a yi mini adalci ba, ni ban iya gori akan komai ba balle akan 'ya'ya, amma itama ai ta haihu me yasa take ko'karin ta karfi sai ta raba ni da yarana. Wannan wata hanya ce da ta 'bullo da ita mai wahalar ganewa domin ni har ga Allah tunda ka auri matar nan ba zan ce maka ga abinda tayi mini na rashin kyautawa ba, idan har ma na fadi wani aibunta na yi mata sharri. Amma ta bullo da wani lamari da zai sanya mini shakku akanta ya za a yi ta k'wace mini yarana kai kuma ka dinga goyuwa da bayanta a ganinka kun yi mini adalci ko kuma dangin Babansu."
Ya yi shiru d'an wani lokaci kafin ya furta." Ki yi hakuri giwa ba wai ina goyuwa da bayanta ba ne a a Ina so na nuna mike cewa duk wanda ya nuna k'auna ga abinka kai yake so, Maryam bata da mummunan nufi akan ku balle yaranku. Ai na d'auka abinki abina ne, ban haifi yaran ba amma tunda ta tsatsonki suka fito wallahi tallahi ji nake yi kamar ni ne ubansu. Ki yi hakuri idan har hakan lefi ne, kuma kin ji hakan bai kwanta miki a rai ba yaranki za su dawo hannunki."
Yadda yake magana cikin kulawa da taushin harshe sai ya d'an ba ni tausayi kuma na tabbatar da cewa abinda ya fad'a akan yaran gaskiya ne domin ya nuna a aikace. Na goge kwallar da ta ciko idona na furta." Ai ban isa ba, idan har ka dawo mini da su za ka iya kiran Baban Saude ko anti Yagana ka gaya musu abinda ban yi ba. Ku ri'ke su kawai kai da ita Allah Ya kula mini da su."

Ya furta." Saboda ni mak'aryaci ne ko? ai magana za mu yi dake anan domin mu samu matsaya ba na so ki yi ta kallona da Maryam a matsayin masu son zuciya na ce idan hankalinki bai kwanta ba zan kawo miki yaranki kalas."
Girgiza kaina na yi tare da cewa." A a fa na bar muku wallahi Allah Ya raya su."
Ya yi shiru yana ta kallona ina goge hawayen da suka kasa tsayuwa. Sai ya matso kusa da ni yana fad'in." Maryam son yarana ne da ita Amina idan na gaya miki yadda take hidima da gidan marayu sai kin yi mamaki ko'ina hannunta yana zuwa ba zata cutar da su ba."
Hanci na ja na ce." To." Sai ya rungume ni tsam a jikinsa yana fad'in." Yi shiru Giwata daina kuka ai nasan kin yi mini sadaukarwa na gode miki Allah Ya yi mini albarka.'' Ya fad'a yana dan shafa bayana. Shiru d'akin na dan wani lokaci kafin ya ce.'' Kamalu zan yi alfahari da shi ga dukkanin alamu domin zamanshi gidan Momi ya fara wanzar da alheri koyaushe cikin koyar da 'yan uwansa hukunce-hukuncen addini yake yi, wannan dalilin ne ma ya sanya ni da ita Maryam din muka yanke shawarar kai shi makaranta ya samu takardar secondary kafin mu tura shi can makarantar da Salim yake karatu. Sannan akwai massalacin dana gina yanzu haka ma mukkulin yana hannunsa domin wancan satin aka yi addu'ar bud'e shi ko ba na gari shine zai cigaba da jan ragamar massalacin kwanaki uku kenan mun fara bin bayansa sallah."
Na daga kai ina kallonsa da sauri na ce." Kamalun kuke bi sallah guda nawa yake ?"
Sai ya yi murmushi yana fad'in." E, ai ya kai munzali kuma ya ilimantu a mu'amula da aikinsa sannan ya balaga uwa uba ya fi da yawa wad'anda suka bin bayansa a sallah ilimi da sanin al'kur'ani yaron da yake da haddar izzu sittin a kansa a malami ne, ko dai kin raina ilimin nasa ne?"
Na girgiza kaina a hankali na ce." Ban raina ba smma abin ne da ban mamaki gaskiya."
Ya ce.'' babu mamaki da ikon Allah Amina ki godewa Allah kawai amma yaron nan ya samu horo kwarai wannan dalilin ma ya sanya ni jin sha'awar taimakawa makarantar iyakacin bakin kokarina."
Na yi shiru ban ce komai ba cikin zuciyata dai ina ta tasbihi ga Allah. (Kalubale ga iyaye mussaman wad'anda yaransu suka taso da fitina kada bakinku ya saba da zagin yaro ko aibata shi da jifansa da kalmomi masu muni. Lallai Allah yakan jarrabi bawa ta hanyar da yaso yakan kuma sanya farinciki da yaye damuwa ta duka hanyar da ya so. Ubangiji Allah Ya shirya mana zuria.)

To tun bayan rarrashin da ya yi mini akan lamarin da ya sake kutso mini na d'an samu sasaauci a cikin raina. Na sake samun kwanciyar hankali kwarai a koyaushe idan Kamalu ya shigo mini cikin tsafta da kamala tare da nutsuwa babu wata damuwa ko kaidaici a tare da shi.Sai dai bangaran Hauwa kam kadaran-kadahan bata ce komai ba amma ko hirar Momi a ke yi a gidan har a gama uffan ba za ta ce ba sai dai ta yi ta jan tsaki. Itama ya d'auke mata Khalil ya mayar da shi can ta dai daure ba ta yi bore ba ban dai sani ba ko sun haura ita dashi kafin faruwar hakan. Twins ne kawai a gidan muke tare

da su tunda suna bakin nono. Su din ma wasu lukutan sukan jima a gidan har sai sun bukaci nono tukkuna za a dawo mini su.
**
Haka ni da ita muka cigaba da safara ba mu Legos ba mu abuja muna raba wattani shida ita kuma Momin tana Abuja tare da yaran domin koda na yaye twins ma gidanta suka koma gabad'aya domin nan ne ya zama matattara ta yara, kuma sun yi bala'in sabo da ita da masu aikinta..

Bayan shakara biyu. Hauwa tana da yara biyu Khalil da mai sunana domin tun ranar da ta haihu uban ya yi mata huduba da Amina sai muke kiranta da Minal.

Ni ma nake samun wani cikin bisa tsautsayi da kaddara ya fita sakamakon wani mugun zazzabi da na yi mai zafin gaske lokacin duka bai fi sati shida ba. amma cikin ikon Allah fitar cikin da wata daya na sake samun wani lokacin ina tare dashi a legos. Sai ya ce sai na koma abuja Hauwa ta zo. Dana tambaye shi dalili kawai sai ya ce a gidan Baby Aish ta rasu haka zalika ma a gidan na samu matsalar ciwo mai zafi har cikinsa ya zube hankalinsa bai kwanta ba. Maganar ma sai ta ba ni dariya amma na daure ban yi ba, saboda Ina gudun ya mayar da abin rigima ina dai ta nazari akan tunaninsa kamar akwai rashin tauhidi a ciki, baby Aish ga abinda ya assasa mutuwarta. Ciki kuma da na samu ya zube wannan kuma ni dashi ba zamu taba cewa ga musababi ba, iko ne na Allah, kuma a dai gidan ai na samu cikinsu Hassana da Husaina gashi duka watanmu  hud'u da zuwa ya Hauwa za ta d'auki lamarin tunda gaskiya yanzu muna zama na fahimtar juna. Ya ce da kansa zai yi mata bayani dalilinsa. Jin haka ya sanya na ce masa ba azanci ba ne yin hakan, kenan ita ba mutum ba ce, idan har yana zargin gidansa da matsala sai ya canza ba zai yiwu a ce saboda na samu ciki har ya samu matsala ya ce daga gidan ne idan ba rikici da neman tashin hankali ba. Ya ce itama tana samun wani cikin sai ta dawo.
Ganin ya'ki fahimtata ya sanya na k'yale shi domin kuwa ko bayan hali akwai girma da nauyin shekaru da suka fara turawa, yanzu nan sai ya rikice mana.

Aka yi sa'a, Hauwa ba ta yi gardama ba. kwananmu biyar da dawowa abuja suka juya tare dashi. Dama Khalil tuntuni ya bar hannunta da Minal kawai ta tafi tunda tana shan mama. Bata yaye ta ba tukkuna.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN▯*

*80*
Ni da baba Tabawa muka cigaba da zama a gidan. Sa'i da lokaci yaran shigo mussaman a ranakun da babu makaranta su d'an yi mana yini kafin su koma. Na cigaba da rainon cikin da yake mugun ba ni wahala duk na k'okale laulayi ya tisani a gaba. Don ma gidan babu wata hidima da yawa ni kuma wani lokacin ba abinci nake iya ci ba. Baba Tabawa itace ke hidimar yi musu abinci da masu gadin gidan da Masa'udu direbanmu na nan.
Nakan zauna na yi ta mamakin yadda baiwar Allan nan ta had'a kan yara wanda ta haifa da wanda bata haifa ba ta ri'ke duka. Irin rikon da take yi wa yaran nan ko ni uwarsu albarka yadda zuciyata take raya mini mummunan nufi akan abinda take yi ba tsakani da Allah ba ne na'ki aminta, domin babu wata alama ta mugunta da ta ta'ba nunawa akan yaran wanda zan gazgata hasashen zuciyata.
Na kan zauna na yi ta tunani akan hakan wataran har na share hawaye idan zuciyata na kissima mini zarginta.  To me ta yi mini idan ba alheri ba, muddin na cika 'yar halak kuwa duk irin abinda zuciyata ke raya mini akanta na yi tsalle na dire na ce ba haka ba ne. Amma wani abin mamaki a wasu lukutan sai na dinga jin mugun haushinta da kishi mai tsanani mussaman idan na tuna yadda maigidan yake bada muhimmanci kwarai da gaske akan abinda ya shafeta.
Ni dalilin alherinta a gare ni  nakan kawar da kaina na mayar da komai ba komai ba ne, amma Hauwa kuwa ba ta iyawa sun sha yin fad'a akanta don bata iya jurewa ba. Wasu lukutan ni nake shiga tsakani na nuna masa cewa duk sanda zai yabi matarsa ya daina yi a gabanmu zuciya bata da k'ashi. Amma ya'ki dainawa. Hauwa ba ta fi ni jin takaicin abinda yake yi ba, kawai ina daurewa ne, kuma ba ta fini kishinsa ba. Idan har muka ce zamu hade mata kai mu biyu abin ba zai yi kyau ba, shiyasa dai nake ta jurewa. Amma na soma yarda da maganar da kullum take gaya mini cewa duk abinda take yi akan yaranmu ba tsakani da Allah ba ne. Shi kansa maigidan ta d'aure shi, kuma baya ta'ba zuwa ya gaya mana ta yi masa lefi duk kuwa da cewar suna samun matsala mussaman ta fannin auratayya ni ina ganewa.

***
Dawowar Salim daga karatu abubuwa suka fara lalacewa. Shine yaronta na biyu bayan Nusaiba itace babba sau daya kacal ta ta'ba shigo wa ta gaishemu, Shima kamar an yi mata dole Shekara daya da wani abu yanzu bata sake shigowa ba duk kuwa da cewa tana yawan ziyartar uwar akai-akai, sa'i da lokaci idan ta zo su Yusi sukan shigo da yaronta, amma dai ita kam ba ta da fuska da fara'a, irin na Mamanta.

Kwana biyu da dawowar yaron muna zaune ni da Baba Tabawa a falo muna hira, gefe kuma muna d'an ta'ba kallo a tibi da yake Baba Tabawa ma'abociyar son kallo ce dalilin da ya sanya ma kenan wasan kwaikwayon dadin kowa baya shigeta. Yanzu ma shi tashar arewa24 din suke haskawa. Kamalu ya shigo tsaf dashi cikin Pakistani da yake ire iren kayan da uwar rikon nasu ke sayarwa kenan, duk rabi kayan ma da suke sanyawa irinsu ne

da jallabiyoyi wattanin bayane ma na ga ta yi musu sabbin 'dinkunan shaddodi da yadika. Sune sanye a jikinsa kansa da farar hula mai raga. Tun da ya shigo nake nazartarsa. Yana zama a gefena k'amshin turaransa ya kama mini hanci. Na zuba masa ido Ina kallo ban ce komai ba.
Ya dube ni a nutse kafin ya ce." Mama mun yini lafiya?"
Na amsa da "Lafiya lau ina Momin?''
A takaice ya furta." Na bar ta a gida, lafiyarta lau."
Ya dubi Baba Tabawa da take ta tsokanarsa da yake da sheik take kiransa irin yadda taji maigidan na kiransa. Itama Momin hakan take ce masa. Ya yi 'yar dariya yana gaisheta ta amsa tana fad'in." Mai zaka ci anan din duk da nasan dai Momi ba za ta barka malami da yunwa ba."
Ya ta'ba cikinsa yana dariya ya ce." Aikuwa kamar kin sani wallahi tare ma muka ci abincin rana a koshe nake. Amma da daddare dai zan ci kwad'on zogale."
Ta ce." Idan wannan ne ai mai sau'ki ne, zan yi maka in sha Allahu."
Ya ce." Na gode Baba."
Daga haka sai ya shiru bai sake magana ba, ya fito da sabuwar wayarsa Samsung da Momin nasu ta saya masa ya fara dubawa fuskarsa babu walwala.

Shiru falon ya yi. Daga ni sai shi domin Baba Tabawa ta shiga kicin domin dora sanwar dare. Kamalu tun yana yaro yake da wani irin hali na bakar zuciya da fushi. Wannan dabi'unsa ne raunanarsu kuwa yana da ala'ka da tafiyarsa karatu da kuma shekarun girma. Amma ba haushe ya ce idan ka jima ba ka ga mutum ba, to duk ranar da kuka hadu ka tambayeshi halinsa. Ni na haifi abina nasan halinsa ciki da waje. Yana da mu'amula ga wanda ya so su yi mu'amular. Amma baya jurar wulakanci a ko'ina ne, akan hakan suka dinga fad'a da Turmizi a can baya.
Duk da har yanzu bai fad'a mini abinda yake damunsa ba, ni da kaina na karanci damuwa mai yawa a tattare da shi. Amma ba zan ce masa uffan ba har sai ya magantu tukkuna."

"Mama ina ta kiran Lambar wayar Baba Hamusu bata shiga tun safe fa." Ya fad'i maganar yayin da yake kallona da wani irin yanayi.
Na ce." Wata'kila network ne, amma Hamusu ai baya kashe wayarsa, ko jiya da yamma mun gaisa."
A sanyaye ya ce." Ina tsammanin hakan."

"Neman me kake yi masa ne?'' Na fad'a idona a tsaye a kansa. Bai dube ni ba ya furta." Ina son zuwa kano din ne na kwana biyu a wurinsa" Na ce." To ka gayawa Baban?" Ina nufin maigidan.
Ya gyada kansa a nutse ya ce." E jiya naso na sanar masa kuma sai na manta, kuma mun yi waya fa, amma dai zan gaya masa ina jin tsoron ya ce a a ne Mama."

"Ka dai gaya masa mu ji mai zai ce, itafa Momin taku?'' ajiyar zuciya ya sauke a hankali ya ce." Mun yi maganar dazu har ta fara had'a mini tsaraba." Shiru na yi kawai ina kallonsa. Har yanzu yanayinsa bai canza ba. Na ce." Kaga ka gaya mini dalilin da zai sanya ka zuwa kano ina tsammanin ai baku wani jima da zuwa ba ko ba haka ba ne?"
Shiru ya yi bai ce komai ba sai da na sake maimaita maganarta sannan ya ce." Eh kafin tafiyarku legos ke da Baba muka je wata shida kenan yanzu. Mama ba na tsammanin zan cigaba da zama anan, can wurin Baba Hamusu zan koma?"

"Akan wane dalili?'' Na fad'a ina kallonsa. Wannan maganar za ta iya janyo rikici a gidan, ta kuma janyo mana b'acin rai ni da shi, abinda maigidan ya tsana kenan. Ya dai yarda dai ya sanya akai su su yi kwana biyu gidan Gwaggo kwana biyu gidan Hajja a dawo dasu wajan matarsa. Ni kuma ba ni da damar magana ko da ta maslaha ce sai ya juyata ya yi ta neman rigima yana fad'in don ba shi ya haifesu ba zan nuna masa iyaka, zan nuna masa bai iya ba, duk yadda zan yi masa misali ba zai gane ni ba, karshe ma sai ya ce zai kira Baban Saude dole nake jan bakina na yi shiru na kyale shi.

Gudun aure paid book ne kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba

"Mama ba zan rufe miki ba, tunda Salim ya dawo daga karatu yake yi mini wasu abubuwa na rashin kyautawa da nuna k'yama. Ba zai ci abinci tare da ni ba, ba zai kwanta d'akin da nake ba, haka zalika a cikin kwana biyun nan baya bina jam'in sallah a massalaci, ina kallonsa ya ke tafiya wani massalacin na daban. Ban san menene dalili ba, Mama amma kuma baya nunawa Yusi k'yama, wannan dalilin ya sanya ni yanke shawarar barin gidan gabad'aya domin ba na so watarana na kasa jurewa muddin a haka zamu dinga tafiya dashi babu kyakykyawar ala'ka, babu musabaha da girmama juna sai k'yama, zuciyata ba zata iya jurewa ba, Ina jin tsoron mu yi fad'a hakan ya ta'ba zumuncinku da zamantakewarku. Kin ga Momi babu komai a tsakanina da ita sai alheri Ina sonta sosai wallahi irin yadda nake sonki Mama, amma ba na so mu yi abinda duka zai bata muku rai shine dalilana."

Nasan dama ruwa baya tsami banza. Amma kuma sanin da na yi wa yaron a baya kafin ya tafi karatun ba haka yake ba. Yaro ne mai nutsuwa da son mutane irin d'an uwansa Adam ga barkwanci. Nusaiban dai ce mara fuska.
Na daure ban nuna b'acin raina a fili ba na ce." Kenan ba ku taba magana ba tunda ya dawo?"
Ya ce." Idan na mik'a masa hannu domin musabaha baya kar'ba. D'azu da safe a gaban Momi ya y hakan ya 'bata mata rai sosai ta yi masa fad'a. Shine ya tashi ya fita bai dawo ba har na fito, wallahi mama kada ki so ki ga yadda hankalinta ya tashi, shine take cewa kada na gaya miki."

Shiru na yi ina nazarin al'amarin. Kamalu bai yi lefi ba domin kuwa anan ya yi aiki da hankali da kuma iliminsa. Na kuma ji dad'in abinda ya yi da har ya iya danne zuciyarsa bai biye masa ba. Shawarar da ya yanke itace mafita muddin kuwa ana son zaman lafiya. Idan har Salim bai gane abinda yake yi kuskure ba ne, to babu mamaki wataran gagarimar matsala ta faru tunda ni nasan wanene Kamalu a fagen zuciya.
Amma yadda zan yi na sanar da maigidan halin da ake ciki shine matsalata. Na riga nasan rikice ne akwance domin kuwa baya d'aukar abinda ya shafi matarsa da wasa. Maganarsa daya amanarsa ce 'ya'yanta ma amana ne, a wannan ga'bar kuwa ya zame masa dole ya bincika domin tabbatar da gaskiyar abinda yake faruwa ya kuma gyara matsalar kafin ta yi nisa.

Na ce." Abinda za a yi yanzu shine ka d'an daure kad'an, ai ni ka burgeni sosai da har ka yi irin wannan tunanin wannan ya sake nuna mini cewa Kamaluna ya bambamta sosai da wanda na sani a baya. Ka cigaba da yi masa magana kada ka biye masa ni kuma zan yi magana da Baban nasan dai haka kawai ai ba zaka kirkiri karya don jin dadi ka gaya mini ba ko?''
"Wallahi Mama babu karya cikin maganata gaskiyar abinda yake faruwa na gaya miki, menene ribata idan na yi k'aryar kuma me ya yi mini da zan 'bata shi."
Na ce." To kada nunawa Momi damuwarka a fuska ka daure ka ji ko."
Ya ce." In sha Allah Mama.
Daga haka sai muka bar maganar muka shiga wata ina d'an jansa da wasa duk domin ganin ya manta abinda yake damunsa. Amma zahiri ni a can 'kasan zuciyata cike nake da fargabar yadda zan tunkari maigidan da maganar. Wala'ala ya fahimceni, wala'ala kuma ya juya mini manufa, amma dai tun yanzu ya kamata a ce ayi wa tufkar hanci kafin lamarin ya yi tsamari rayuka su zo suna 'baci.
Daf da magriba ya tashi  ya fita da zummar shirin shiga massalaci.

Bayan kwana biyu ina cikin nazari domin har yanzu na kasa tsayar da abinda nake ganin shine daidai. Ba na so na yi magana ne a ce na goyi da bayan yarona wata'kila shi kansa zai iya ganin haka shiyasa hankalina bai kwanta ba har yanzu sai dai na gaza daurewa na sanar da Baba Tabawa abinda yake faruwa domin kuwa macace mai tsinkaye da nisan tunani.
Ta jima tana jimantawa kafin ta ce." Ai shurun ba shine mafita ba, gwara ki gaya masa tunda shine jagoran kowa a gidan ya yi wa tufkar hanci kada lamari ya yi k'wari hatsaniya ta tashi ya ce mai yasa ba a gaya masa ba. Ina ganin duk wanda zai ce kin so kanki da zummar kawo gyara to ya zalinceki domin kuwa abinda ki ka yi shine daidai, ai ba ki za'bi Kamalu kin fifita  akan Salim ba, duka naki ne kamar yadda itama Momin take nunawa, to ya kamata a ce wannan 'barakar da take ko'karin kunnowa an yi maganinta.

Ajiyar zuciya na sauke bayan duk na gama saurararan maganganunta. Na ce." Shikkenan Baba, in sha Allah zan sanar da shi halin da ake ciki duk kuma yadda muka yi aki ji."

Ta ce." To shikkenan, Allah Ya maganta."
To daddare ina d'aki a kwance misalin takwas da rabi ya shigo mini cikin tsananin b'acin rai. Na tashi zaune da sauri gabana na fad'uwa. Ya zauna samar kujerar madubi na ce." Kai lafiya Kamalu."
"Mama barka da dare." Da abinda ya fara kenan. Na amsa a takaice na ce." Menene?"
Duk dauriyarsa sai da muryarsa ta yi rawa ya ce." Mama ba zan iya ba, ba zan iya jurewa ba, zan tafi kano gobe domin kuwa Salim baya neman zaman lafiya da ni."
"Mai ya yi maka kuma?" Na tambayeshi jikina sanyi kalau domin kuwa wani yanayi na shiga na tsananin tausayin yaron ba komai ne ya janyo masa hakan ba sai maraici da rashi domin kuwa duk abinda Salim yake yi yana yi ne domin ya ga a cikin rigar arziki su yake.

"Salim tare da abokansa suke yi mini dariya har na ji daya daga cikinsu yana kirana da 'kolo, dayan kuma yana cewa mini criminal." Sai hawaye suka fara kasa tsare a kumatunansa.....

Chapter 29 Bata kai kalma 2k yanzu na cika she muku a wannan chapter din.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*81*
Zuba masa ido na yi ina kallo a yayin da hawayen ke ta zarya a dakalin fuskarsa bai goge ba, ni ma kuma ban ce masa ya yi shiru ba sanin da na yi cewar kukan shine zai sassauta masa takaicin abinda aka yi masa. Lallai gagarimin abu ne ke sanya fitar hawaye a idon Kamalu tun yana yaronsa balle yanzu da shekarun samartaka suka fara kama shi dole an yi gwagwarmayar rayuwa a samu zuciya ta sake 'ke'kashewa.
Idan an kira shi da 'kolo (almajiri) ai ba damuwa ba ne, ni na ji dad'i ma da ya zama 'kolon mahaddaci kuma marubucin al'kur'ani. Kalmar criminal din ce ta hargitsa dukkanin lissafina, Salim abin har ya kai haka. Abinda ya faru shekaru kusan shida zuwa bakwai yaro ya samu nutsuwa ya zama mutum shine yanzu za a tayar masa da hankali.
Cikin jan ajiyar zuciya ya ce." Mama Salim na b'akinciki da yadda Allah ya yi mini jama'a a area nan, sannan yana kishi sosai ya ga na bude massalaci manya mutane na bina sallah suna gaisawa da ni. Wannan na ji da kunnena

yana fad'in duk wanda ya bi b'arawo sallah shi ma bashi da maraba da 'barawo, kuma sannan bashi da sallah. Mama yaushe wannan sunan zai goge a tarihin rayuwata"
Na ji kwalla ta ciko mini ido. Na daure ban yadda ta zuba ba, na ce." To share hawayenka ka daina kuka ka ajiye abinda yake faruwa a matsayin cigaba, domin kuwa haka siddin ba zaka cimma wata nasara ba tare da kalubale ba. Ita hassadar ai itace matakin komai. Kada ma ka damu, kuma ina mai tabbatar maka da cewa watarana Salim zai bi ka salla, zai kuma nemi fatawa a wurinka, wannan ni ce na gaya maka, domin kuwa ina nan ina roka maka d'aukaka da shura ta fanninin addini anan gidan duniya, Kamalu idan Allah Ya yarda duniya da mutanan dake cikinta za su amfana da kai."
Hannu yasa ya goge hawayen dake zuba a kumatunsa. Na ce." Ka kyale mini komai a hannuna, ka ji ko ka cigaba da hakuri, ni kaina a wannan ga'bar ba zan ha'kura ba dole a yi wani abu kai, amma kada ka nunawa Momi komai, ka bar abin a zuciyarka."
A sanyaye ya ce." Shikkenan Mama, zan yi yadda ki ka ce din, amma ni ina so na koma can kano zan fi samu nutsuwa cigaba da gudanar da neman ilimina."
Na ce." Idan har hakan shine alheri za ka koma Kamalu, ka cigaba da addu'a ka kuma bar maganar tsakanina da kai."
To a daran na nemi maigidan a waya duk da nasan ba sosai yake amsa waya da daddare ba amma yadda nake jin zuciyata ba zan iya bari sai gari ya waye ba. Wayar ta katse bai daga ba sai na yi masa text na cewa ina son magana dashi a duk lokacin da ya ga sakona.
Wajan goma da rabi kuwa ya kira ni da kansa. Na daga muka gaisa a nutse.
Na ce." Baba ina son magana da kai amma kada ka fahimce ni girman Allah da Annabi ka dubeta ta fuskar hankali da maslaha."

A nutse ya ce." To ina jinki ai ni mai hankali ne ba mahaukaci ba, kada dai ki ce mini kin yi 'bari domin kwana biyun nan mafarkai nake yi marasa kan gado, Ina ganin ma farkon watan nan za mu zo."
Na ce." Ban yi 'bari ba, amma ka sani cewa ni da kai ba mu da ikon komai akan abinda Allah Ya zartar. Idan har kaddara ta gifta cikin ya samu matsala ba za ka d'auki kaddara ba kenan?"
Ya ce." Zan d'auka mana, ai mafarkan da nake yi ne ya sanya ki ka ji na yi miki wannan maganar. Na tuba ga Allah duk yadda ya yi daidai ne."

Shiru na yi ina sauraransa har ya gama maganganunsa. Na ce dalili ne mai karfi ya sanya ni kiranka a daran nan, kuma ni kaina zan ji dadin zuwanka domin ka gyara abinda yake faruwa Kamalu ne da Salim....... Duk abinda yake faruwa na zayyane masa. Ya jima yana nanata maganar da mamaki mai yawa a tare dashi ya ce." Yaushe Salim ya lalace haka, kuma abu ya faru tunda kuruciya saboda rashin hankali ka tara abokai kana gaya musu criminal?" Ya sake maimaita kalmar tabbacin hakan ya bashi tsoro da mamaki.
Na ce." Kamalu ya ce zai koma kano da zama can wurin Hamusu."

Gyaran murya ya yi tare da cewa." Wannan kuma abinda yake cikin ranki ne shekara da shekaru shine ki ka samu mafaka dalilin wannan matsalar. Na gaya miki Amina idan har Kamalu zamansa zai koma kano to Yusi ma zai bi shi. Nusaiba da Salim Adam amana ne a hannuna. Haka zalika tunda ina auranki yaranki ma amana ne a hannuna koda ubansu yana raye to balle kuma baya raye. Idan har kina ganin za ki yi iko da abinki ni ban iya ba sai na ce Allah Ya taimaka."
Na ce." To yanzu ya kake so a yi? Kasan dai cigaba da zaman Kamalu a gidan Momi akwai matsala watarana za su iya yin abinda bai da ce ba."
"Babu abinda zai faru, ki kyaleni da yaran dukkaninsu tunda kin gaya mini kin gama aikinki."
Jiki babu karsashi na ce." Shikkenan sai da safe." Sai kawai na kashe wayar domin kuwa jikina yana ba ni kamar ba zai d'auki tsatstsauran mataki ba.
Da lamarin na kwana na kuma wayi gari dashi dalilin da sanya kenan na kasa barin abin iyakacinmu. Na kira anti Yagana na gaya mata halin da ake ciki. Sosai kuwa ranta ya 'baci ta dinga fad'a tana cewa babu lallai babu dole muddin da cin zarafi da cin mutuncin da kuma tozarci Kamalu dole ya bar gidan.  Arziki ai ba hauka ba ne.
Na ce." Anti Yagana tun farko fa ni dama abinda na guda kenan, shiyasa da matar nan ta bukaci zaman Kamalu a wurinta na dinga gocewa. Karin abin kuma maigidan ya'ki ya fahimceni, wai muddin Kamalu zai bar gidan sai dai su tafi da Yusi wanda na tabbatar da cewar hakan matsala ce babba. Da ya zauna mun yi magana da fahimta tuntuni da tun farko wannan matsalar bata kunno kai ba.  Abu na biyu kuma ga yanayin bayanin da Kamalu ya yi mini yadda na fahimta shine shi Salim yana adawa da yadda Allah ya d'aukaka Kamalu fiye dashi, ai nasan yaron yana da kirki tun kafin ya tafi karatu dawowarsa al'amura suka lalace kishi ne shi mai yasa Allah bai yi masa ba."
Ta ce." Wannan kuma Ubangiji zai kalubalanta. Wace irin wahala da gwagwarmaya ce Kamalu bai sha ba. Yanzu kuma Ubangiji Allah Ya d'aukaka darajarsa wannan duka ba dabararmu ba ce ikonsa ne, gaskiya a wannan ga'bar ni ma bana goyan bayan mijinki Amina Kamalu dole ya tafi ya bar musu gidansu  idan sun ce ba haka ba sai ya dawo hannunki shine karshen magana."

Na ce." Anti Yagana ni na fi so fa ya koma kanon ko ya dawo nan wurinku hankalina zai fi kwanciya gaskiya, domin ai ko yana gidana ba a kashe matsalar ba tunda duk lokacin da ya fita zai iya yin karo da Salim da abokansa  kin ga matsalar ai bata mutu ba."
"To ni da kaina zan kira Yallabai din a waya na bashi shawara yadda za a yi. Ta fad'a tana nishin 'bacin rai."
Jin haka ya sanya na ce." Kada ki kira shi yanzu anti Yagana mu bari ya zo mu ga hukuncin da zai yanke idan babu adalci sai ki yi masa magana."
Ta ce." Shikkenan haka za a yi in sha Allah, na manta ma ban gaya miki ba shekaran jiya amaryar Babandi matar da ya aura ta uku ta haihu." A takaice na ce.'' A yi masa barka Allah Ya raya, domin ni yanzu ko lambarsa ma ba ni

da ita yadda maigidan ya tsaneshi haka ya tsani mutuwarsa shiyasa na goge lambarsa daga wayata a gabad'aya duk domin a zauna lafiya.
**
Bayan sati biyu al'amura suna cigaba da tafiya da dad'i babu dad'i. Har zuwa lokacin Salim bai kyale Kamalu ba. Kusan kullum da b'acin rai yake shigo mini duk da yana ko'karin daurewa amma ina fahimta. Ha'kurina yana daf da k'arewa domin tun ranar da na kira maigidan a waya na gaya masa abinda yake faruwa bai sake nema na da maganarba duk kuwa da cewa kusan kullum sai mun yi bidiyon call. Ni ma ban sake tayar da maganar ba na bari ne kamar yadda ya ce mu jira zuwansa. Amma koyaushe idan na dubi Kamalu na ga yadda ya rage walwala da kuzari zuciyata takan yi zafi. Ina dalili haka kawai saboda gudun b'acin ran wani a 'kuntata zuciyar yaro. Babu lallai fa babu dole muddin ba zai d'auki mataki ba wallahi sai Kamalu ya tafi ya bar garin da gidan gabad'aya.

Gudun aure littafin kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ranar litinin da yamma suka sauka shi da Hauwa. Baiwar Allah ta kuma samo wani cikin domin yanayinta kadai ya tabbatar mini da cewa laulayi take yi ta yi mugun haske dama idan tana da ciki d'ashewa take yi. Macace mai kwainika Minal na da wata goma sha takwas. Allah Ya sa tana da san girma, tana yawo da kafafunta da yake abincin gwangwani take ci a can ta zama rusheshiya kataf-kataf haka take yawo uban yana tsokanarta da 'yar sukuta. ko ya kira ta da giwa wai na washeta har ta fi su Hassana girma jiki tunda su jikin irin nasa ne. Kwana biyu da zuwansu na fahimci rashin jituwa a tsakaninsu. Kamar ma basa magana da juna. Na yi dai shiru ina kallon ikon Allah. Ita yini ma take yi a d'aki sai yamma take fitowa falo shi kuma har ya yi kwana biyunsa a wajena bai ce mini komai ba.
Na cika da mamaki sosai. Lallai ma wannan mutumin wato maganar tabi shanun sarki kenan Salim ya yi daidai babu kuskure akan abinda yake yi.
Ba zan lamunta ba domin kuwa har yanzu a cikin matsalar ake sai abinda ma ya yi gaba. Kamalu bai rasa madogara ba hakama Yusi idan har ba zai gyara abinda yake faruwa ba to na yarda ya ba ni yarana su kuma can hannun Babansu Hamusu.
Cikin wannan nazarin Hauwa ta shigo d'akina ta same ni. Ta zauna gefan gado tana fad'in." Ko jikin ne?" Na tashi zaune Ina fad'in." A, a ni kam ai na warware na bar miki Hauwa."
Kwafa ta yi tare da cewa." Ban ji dad'in shigar cikin nan ba wallahi.''
Na dubeta a tsanake tare da cewa." Mai yasa Hauwa ki godewa Allah da fatan samun masu albarka."
"Humm!" abinda ta ce kenan kafin ta ce." Ban shigo domin na tunzuraki ko tayar da husuma ba. Idan kin lura da yanayin yadda muka zo da ni da maigidan babu dadi don wallahi mugun haushinsa nake ji fad'a muka casa tun a can."

Na ce." Menene kuma ya kamata ki manta da matsalar matar nan Hauwa, ki yi ta kanki haihuwa ta uku za ki yi da mutumin nan duk abinda zai yi ya je ya yi haka ya ga zai iya."

"Wallahi Amina ko kaffara ba zan yi ba matar nan ba haka ta bar mutumin nan ba."
"Mai yasa ki ka ce haka Hauwa, zato zunubi ne fa koda ya kasance gaskiya ne?"
"Amina maganar gaskiya zan gaya miki na gaji da zaman nan da muke yi na rashin 'yanci da kaskanci wallahi tallahi ba zan jiya jure ba, wannan shine dalilin ma da ya sanya ki ka ji na ce ina b'akinciki da takaicin samuwar wannan cikin na jikina, in banda ina gudun sa'bawa Allah wallahi da sai na zubar da shi.......

*Rikicin gidan Alh Tajo sai dai na ce Allah ya yayyafawa abin ruwan sanyi bari mu ya ya zata kaya....*
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*83*
Na ce." Ai ba ta yi lefi ba gaskiya ta fad'a domin shine zama na amana. Kuma wallahi a yanzu ni Amina Hauwa ta fiye mini kai sau dubu tunda ka nuna mini zahirinka na gani, ni duk wanda za a had'a kai dashi a k'yamaci abina, ba na daukarsa a matsayin masoyi babban ma'kiyi nake kallonsa."

Da wani irin yanayi a tare da shi ya furta." Idan na fahimce ki kenan kina kallona a matsayin ma'kiyinki wanda ya za'bi Maryam da 'ya'yanta ko Amina."
Na ce." K'warai kuwa wallahi tallahi ba ka cikin jerin masoyana tunda har ka iya yadda da cewa Kamalu zai aikata wannan mummunan lamarin. Ba na yi maka kallon masoyi."
Ya jima yana kallona kafin ya gyad'a kansa ya nufo ni, na kuwa zabura domin kallon dodo nake yi masa na ce." Kada ka zo inda nake na rantse da Allah zan illataka."
Bai daina tafiya ba har sai da ya cimmani zai ri'ke hannuna na fizge da sauri na wancakal da nasa hannun cikin zafin nama na yi wajan madubina na zari wata doguwar kwalba ta turare na ri'ke a hannuna. Ya sake nufo ni yana fad'in." To illatani kin ji, na ce ki illatani tunda kin 'ki tsayawa mu fahimci juna. Da k'araji na ce." Har abada na sake aminta da maganar munafiki."

Ya 'bata fuska ainun yana fad'in." Kada kuma ki wuce gona da iri, kin naushe ni a ma'karfafata d'azu na kyale ki yanzu kuma kina kira na da munafiki ranki zai b'aci fa ba ni son rashin hankali."
Na ce." Ya 'baci ma ai ba tsoro nake yi ba, menene karshen hukuncin shine saki ko to ka sake ni kaga yadda ake liyafa ai ni kassara mini rayuwata ka yi zama dakai bai amfanar da ni komai ba."
Ya kuwa 'kadu da wannan furucin ya ce." Har yaran da muka haifa ba su da amfani?" Na ce." E, ai ba nawa ba ne tunda ka d'aukesu ka bawa bushshiyar matarka nata ne taje na bar mata."
Ya dinga kallona da mamaki mai yawa kafin ya sake tunkaro ni a karo na biyu na daga abinda yake hannuna zan buga masa ya yi saurin ri'ke hannun tare da k'wacewa. Muka yi cirko cirko a tsaye shima nishin yake yi kamar yadda nake yi kamar wanda ya yi tsere. Mun jima haka ya ri'ke ni katamau na ja tsaki tare da yun'kurin bangaje shi ya riko kafadata jikinsa duk ya yi la'asar. Na ce ka cika ni na gaya maka
na rantse da girman Allah da Annabi sai yaran nan sun bar hannunka tunda ka gaza ri'ke su tsakani da Allah ko da hakan zai yi sanadiyar rabuwarmu

"Ba ki da hankali har yanzu ko Amina?"
Na ce." E, ba ni dashi tunda kai din shine da kai." Murmushi ya yi ya girgiza kansa yana fad'in." Ke kam kin ci sa'a ina sonki ina ga da babu wannan da tuni mun rabu baram-baram, iskanciki da rashin kunyarki ya ishe ni. Yanzu ni ne mara hankali Amina baki da kunya ba ko."
Juyar da kaina gefe na yi ban ce komai. Sai ya girgiza kansa a nutse ya fara ko'karin jan hannuna yana fad'in." Zo mu je mu zauna domin mu tattauna."

"Ba zan zauna ba domin ba ni son had'a numfashina da kai." Na fad'a tare da buge hannunsa da yake jana. Sai kuwa ya sanya mini karfi ban ankara don kamar tanka'dani ya yi na fadi a da'bas a wurin. Kafin na yun'kura na tashi ya cimmani ya sake tura kirjina da k'arfi na kwanta kaina ya tallafo kawai yasa bakinsa a nawa ya dinga d'ura mini yawun bakinsa ba don ya ji dad'i ko don na ji yake kiss din bakina ba domin ya sanya mini yawunsa ne. Tsayin minti hud'u zuwa biyar ya cire bakinsa tare da tashi tsaye ya tsaya a kaina yana kallona idonsa ya kada sosai da tsantsar tashin hankali a cikinsu.
Na tashi zaune hawaye masu d'umi suna silalowa daga idona. Kamar mai koyon tafiya haka na dinga jan k'afa ina kuka na isa gefan gado na zauna kamar an kwad'e mini gwiwata da tabarya lallai Allah Ya jarrabeni da shu'umin mutum.
Ya biyo ni shima kamar wanda aka kuzawa ruwan sanyi jikinsa duk a sanyaye. Yana zama a gefena na yi kukan kura cikin wani yanayi na bazata na sake kai masa naushi a kirjinsa ya kuwa yi kwanciyar da bai shirya ba na zabura da sauri na d'auki fillo na raba k'afafuna akan ruwan cikinsa na danna masa fillon a hancinsa ina ihun nake fad'in." Sai na kashe ka wallahi, na yarda ni ma a kashe ni, ni ce ajalinka tunda ba zaka bari na huta ba."
Fad'a sosai muka dinga yi tiki tiki yana yun'kurin tashi ina sake turmushe shi nauyina gabad'aya na saki a kansa ina kuka. Cikin tashin hankali da nishi

tare da fitowar numfashi ya fizge a guje ya dira daga gadon yana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Bai fita ba yana tsaye a bakin kofar d'akin ya ki'dime sosai ko da ya ga na sake durfafoshi bai yi yun'kurin bude kofar ya fita ba. Ina isa kuwa ya kama ni da karfin da ban san yana da shi ba. Cikin rawar murya da tsananin damuwa yake fad'in." Yi ha'kuri, ki yi hakuri na ji na yi lefi, amma ki fahimce ni ki bari na gaya miki abinda yake zuciyata kafin ki kashe ni din."
Na yi shiru hawaye na fita daga idona, ina jan hanci na ce ." Wallahi ba zan sake yadda yarana su zauna a hannunka ba" Ya ce."
" Ki fahimce ni Amina, ban za'bi bangare daya na ajiye daya ba. Ni kaina lamarin ya sanya ni a rud'ani ba kad'an ba. Shirun kuma da na yi ba ina nufin na goyi da bayan maganar Salim ba. Ina bincike ne da kuma hanyar da zan kawo gyara. Akwai nauyi mutuka da gaske na tunkareki da maganar nan. Akwai kunya na titsiye yaron nan Kamalu ina neman hujja akan maganar Salim. Kada ki zarge ni bayan ba ki san menene a zuciyata ba.

"Na gaya maka wallahil-azim ba zan yarda da kanzon kurge ba. A wannan ga'bar ko ni ko kai, Kamalu da Yusi fa ba su rasa madogara ba. Sannan Ubansu ba makwad'aici ba ne, ba mazinaci ba ne, sannan ba b'arawo ba ne. Banga dalilin da zai sanya a dinga jingina musu manya manyan sharri ba. Ban nemi ka rike mini yara ba. Haka zalika ma ban nemi matarka ta ri'ke mini yarana ba. A ba ni kayana mana dole ne, zan iya rikesu mu rayu cikin nutsuwa da kwanciyar hankali."

"To ni kuma muddin a karkashin ikona ki ke yaran nan babu inda za su je muna tare har abada, tunda ina tare dake ni ba zan iya rabuwa dake ba."
Na dube shi ina gyada kaina na ce." Haka ka ce ko?''
"Kwarai kuwa, haka na ce, sai ki yi duk abinda za ki yi tunda ke ba za ki rarrasu ba.
"Zan kuwa yi, ai ba kai ka haifar mini su, baka da wani ji'bi dasu don haka baka da hujjar da zakace dole sai ka rikesu anan zan nuna maka karfin ikona."
Ya ce." Sai ki nuna din ina jiranki..'' Daga haka ya cika ni tare da  jan tsaki ya juya ya fita yana fad'in." Sakarai kawai kullum kina girma kina cin tasono."
Silalewa na yi a k'asan d'akin na yi zaman dirshan na dinga tikar kuka. An dake ni an hana ni kuka kuma an bi ni da bakar magana. Wace irin masifa ce wannan mutum bai haifi yara ba ya ce lallai sai ya rike su.
Ina cikin wannan yanayin Hauwa ta shigo sanye da hijabi a jikinta idonta jawur! Na tashi tsaye da sauri Ina kallonta gabana na fad'uwa. Minal ta dire mini a gabana tana fad'in.'' Ga takwararki nan Amina ubanta ya ce na tafi gidanmu."
Cikin kad'uwa da muguwar fargaba na ce." Ki tafi gidanku akan wane dalili Hauwa?"
"Saboda na gaya miki abinda yake faruwa." Ta fad'a tana juyawa da niyyar fita. Na bita da sauri yayin da Minal din ta tawo kataf katafi ta rike gefan hijabinta tana kuka. Na ce." Shine kuma ke sai ki tafi."

"To dama  ai kamar akan 'kaya nake wallahi na gaya miki a gajiye nake." Na ce." Ita Minal din mai tayi miki to?"
"Cewa ya yi na ajiye masa yarinya."
Wani takaici ya yun'kuro mini lallai Alhaji Amadu ya mutu ya bar baya da k'ura. Iyalinsa na nema su tarwatsawa aminin nasa rayuwa. Na tabbatar da cewa ba kowane ya janyo wannan hayaniyar ba sai Salim.
Na ce." Yana ina maigidan?"
"Shi ya sani.'' Ta fad'a a takaice tare da sake nufar hanyar fita.  Na ri'ke hannunta ina fad'in." Babu fa inda za ki je Hauwa."
Dariya ta yi irin ta takaici ta ce." Ai ba ke ki ke aurena ba Amina, maigida ya ce na fitar masa daga gida zaman me zan yi."
Jan hannunta na yi muka zauna kan gado na dau'ki Minal na d'ora mata a cinyarta sannan na d'auki wayata. Kiransa na yi bugun farko ya d'aga kamar yana jira.

Littafin nan na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na ce." Yanzu kai don girman Allah ba ka ji kunya ba, tsofai tsofai da kai kake aikata irin abun yara?"
"Mai na yi kuma? Ke ba kya jin nauyin furta mini maganar da duk ranki ya so ko Amina?''
Na ce." Hauwa dai ko babu aure tana da 'yancin zama na dindindin a gidanka, to balle bayan wannan alakar akwai ta aure da zuria a tsakaninku, da ka ce ta tafi gida kai ba ka ji nauyi ba?"
"Bata da wani 'yancin zama a gidana sai na so, tunda ba ta ji nauyin shure maganata ba, ni ma babu wani nauyinta da zan ji, kuma ina ruwanki matarki ce?"
'Dan sassautawa na yi domin kuwa ba zan so a ce dalilina sun samu matsala ba. Na ce." Idan saboda ta gaya mini wannan maganar nan ya sanya har ka yanke mata wannan hukuncin ka yi hakuri ka ji."
Shiru ya yi bai ce uffan ba. Na ce." Ka janye abinda ka kudirta akanta domin kuwa sam bai dace ba."
"Kin yarda ta yi ba daidai ba yanzu?"
Shiru na yi ban ce komai ba. Ya sake maimaita maganarsa nan ma ban ce masa komai ba. Ya ce." To tunda bakinku daya kin ga kuwa babu amfanin zama da macan da bata buk'atar zaman lafiya da kwanciyar hankali. Hauwa kawai ta tafi gidansu kafin na gama yanke hukunci ta san matsayinta, tunda har za ki iya d'aukar fillo ki toshe mini hanci don na mutu ai lamarin babban ne a wurina Hauwa ta samu nasarar tayar mini da husuma ni kuma zan d'auki matakin da ya dace a kanta."
Gwiwa a sanyaye na kashe wayar ina kallonta babu damuwa a tare da ita tace." Ai na gaya miki Amina mutumin nan kaf dabi'unsa sun canza muddin akan lamarin matarsa ne yakan iya cin mutuncin kowa."

Na ce." Babu da inda za ki je." Ta yi shiru tana kallona ina laluban wayar Hajja bugu daya ta daga. Cikin rawar murya na gaisheta ta amsa tana fad'in duk kuna nan lafiya ko Amina."
Na ce." Lafiya lau Hajja don Allah ki yi masa magana matsala suka samu da Hauwa shine ya ce wai ta tafi gida."
cike da mamaki ta furta." Hauwa ta tafi gida akan wane dalili?"
Shiru na yi ban ce komai ba.
Cike da kulawa ta ce." Amina ki gaya mini menene yake faruwa kin ji ko kada ki rufe mini komai.''
Hawaye suka silalo mini na ce." Hajja Hauwa ba ta yi masa komai ba wallahi, asalima ma matsalar ni ta shafa saboda kawai ta gaya masa gaskiya shikkenan yake jin haushinta."
Ta ce." To gaya mini wace matsala ce, ni zan yi maganinta, Hauwa kuma ki gaya mata kada ta fito."
"In sha Allah, gata nan a kusa da ni, na hana ta fitowa."
"To hakan ya yi ina sauraranki." Tafad'a cikin nuna damuwa. A nutse na fara gaya mata tun daga farko abinda yake faruwa har zuwa yanzu da ake wannan rikicin.

Hajja ta jima cikin alhini da takaici kafin ta ce." Ki yi hakuri a matsayinki na babba kuma uwa. Amina tabbas ko ba ki fad'a ba nasan idan za a tona zuciyarki to tanan cikin kunci da b'acin ran wannan lamari. Ki jure lallai kuma ya zama dole a yi wa tufkar hanci saboda gudun abinda zai afku anan gaba na rashin dadi. Zan nemi shi zai kuma zo nan inda nake akan maganar nan domin ni kaina ban yarda da hakan ba. Sannan duk abinda zai yi muku kada ku saurareshi. Ki jadaddawa Hauwa cewa da yawuna ban amince ta fito ba. Ke kuma ki yi hakuri kin ji ko, nasan abinda da ciwo a zucci amma in sha Allahu gaskiya za ta bayyana kanta.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne  vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*83*
Na ce." Ai ba ta yi lefi ba gaskiya ta fad'a domin shine zama na amana. Kuma wallahi a yanzu ni Amina Hauwa ta fiye mini kai sau dubu tunda ka nuna mini zahirinka na gani, ni duk wanda za a had'a kai dashi a k'yamaci abina, ba na daukarsa a matsayin masoyi babban ma'kiyi nake kallonsa."

Da wani irin yanayi a tare da shi ya furta." Idan na fahimce ki kenan kina kallona a matsayin ma'kiyinki wanda ya za'bi Maryam da 'ya'yanta ko Amina."
Na ce." K'warai kuwa wallahi tallahi ba ka cikin jerin masoyana tunda har ka iya yadda da cewa Kamalu zai aikata wannan mummunan lamarin. Ba na yi maka kallon masoyi."
Ya jima yana kallona kafin ya gyad'a kansa ya nufo ni, na kuwa zabura domin kallon dodo nake yi masa na ce." Kada ka zo inda nake na rantse da Allah zan illataka."
Bai daina tafiya ba har sai da ya cimmani zai ri'ke hannuna na fizge da sauri na wancakal da nasa hannun cikin zafin nama na yi wajan madubina na zari wata doguwar kwalba ta turare na ri'ke a hannuna. Ya sake nufo ni yana fad'in." To illatani kin ji, na ce ki illatani tunda kin 'ki tsayawa mu fahimci juna. Da k'araji na ce." Har abada na sake aminta da maganar munafiki."
Ya 'bata fuska ainun yana fad'in." Kada kuma ki wuce gona da iri, kin naushe ni a ma'karfafata d'azu na kyale ki yanzu kuma kina kira na da munafiki ranki zai b'aci fa ba ni son rashin hankali."
Na ce." Ya 'baci ma ai ba tsoro nake yi ba, menene karshen hukuncin shine saki ko to ka sake ni kaga yadda ake liyafa ai ni kassara mini rayuwata ka yi zama dakai bai amfanar da ni komai ba."
Ya kuwa 'kadu da wannan furucin ya ce." Har yaran da muka haifa ba su da amfani?" Na ce." E, ai ba nawa ba ne tunda ka d'aukesu ka bawa bushshiyar matarka nata ne taje na bar mata."
Ya dinga kallona da mamaki mai yawa kafin ya sake tunkaro ni a karo na biyu na daga abinda yake hannuna zan buga masa ya yi saurin ri'ke hannun tare da k'wacewa. Muka yi cirko cirko a tsaye shima nishin yake yi kamar yadda nake yi kamar wanda ya yi tsere. Mun jima haka ya ri'ke ni katamau na ja tsaki tare da yun'kurin bangaje shi ya riko kafadata jikinsa duk ya yi la'asar. Na ce ka cika ni na gaya maka
na rantse da girman Allah da Annabi sai yaran nan sun bar hannunka tunda ka gaza ri'ke su tsakani da Allah ko da hakan zai yi sanadiyar rabuwarmu

"Ba ki da hankali har yanzu ko Amina?"
Na ce." E, ba ni dashi tunda kai din shine da kai." Murmushi ya yi ya girgiza kansa yana fad'in." Ke kam kin ci sa'a ina sonki ina ga da babu wannan da tuni mun rabu baram-baram, iskanciki da rashin kunyarki ya ishe ni. Yanzu ni ne mara hankali Amina baki da kunya ba ko."
Juyar da kaina gefe na yi ban ce komai. Sai ya girgiza kansa a nutse ya fara ko'karin jan hannuna yana fad'in." Zo mu je mu zauna domin mu tattauna."

"Ba zan zauna ba domin ba ni son had'a numfashina da kai." Na fad'a tare da buge hannunsa da yake jana. Sai kuwa ya sanya mini karfi ban ankara don kamar tanka'dani ya yi na fadi a da'bas a wurin. Kafin na yun'kura na tashi ya cimmani ya sake tura kirjina da k'arfi na kwanta kaina ya tallafo kawai yasa bakinsa a nawa ya dinga d'ura mini yawun bakinsa ba don ya ji dad'i ko don na ji yake kiss din bakina ba domin ya sanya mini yawunsa ne.

Tsayin minti hud'u zuwa biyar ya cire bakinsa tare da tashi tsaye ya tsaya a kaina yana kallona idonsa ya kada sosai da tsantsar tashin hankali a cikinsu.
Na tashi zaune hawaye masu d'umi suna silalowa daga idona. Kamar mai koyon tafiya haka na dinga jan k'afa ina kuka na isa gefan gado na zauna kamar an kwad'e mini gwiwata da tabarya lallai Allah Ya jarrabeni da shu'umin mutum.
Ya biyo ni shima kamar wanda aka kuzawa ruwan sanyi jikinsa duk a sanyaye. Yana zama a gefena na yi kukan kura cikin wani yanayi na bazata na sake kai masa naushi a kirjinsa ya kuwa yi kwanciyar da bai shirya ba na zabura da sauri na d'auki fillo na raba k'afafuna akan ruwan cikinsa na danna masa fillon a hancinsa ina ihun nake fad'in." Sai na kashe ka wallahi, na yarda ni ma a kashe ni, ni ce ajalinka tunda ba zaka bari na huta ba."
Fad'a sosai muka dinga yi tiki tiki yana yun'kurin tashi ina sake turmushe shi nauyina gabad'aya na saki a kansa ina kuka. Cikin tashin hankali da nishi tare da fitowar numfashi ya fizge a guje ya dira daga gadon yana kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Bai fita ba yana tsaye a bakin kofar d'akin ya ki'dime sosai ko da ya ga na sake durfafoshi bai yi yun'kurin bude kofar ya fita ba. Ina isa kuwa ya kama ni da karfin da ban san yana da shi ba. Cikin rawar murya da tsananin damuwa yake fad'in." Yi ha'kuri, ki yi hakuri na ji na yi lefi, amma ki fahimce ni ki bari na gaya miki abinda yake zuciyata kafin ki kashe ni din."
Na yi shiru hawaye na fita daga idona, ina jan hanci na ce ." Wallahi ba zan sake yadda yarana su zauna a hannunka ba" Ya ce."
" Ki fahimce ni Amina, ban za'bi bangare daya na ajiye daya ba. Ni kaina lamarin ya sanya ni a rud'ani ba kad'an ba. Shirun kuma da na yi ba ina nufin na goyi da bayan maganar Salim ba. Ina bincike ne da kuma hanyar da zan kawo gyara. Akwai nauyi mutuka da gaske na tunkareki da maganar nan. Akwai kunya na titsiye yaron nan Kamalu ina neman hujja akan maganar Salim. Kada ki zarge ni bayan ba ki san menene a zuciyata ba.

"Na gaya maka wallahil-azim ba zan yarda da kanzon kurge ba. A wannan ga'bar ko ni ko kai, Kamalu da Yusi fa ba su rasa madogara ba. Sannan Ubansu ba makwad'aici ba ne, ba mazinaci ba ne, sannan ba b'arawo ba ne. Banga dalilin da zai sanya a dinga jingina musu manya manyan sharri ba. Ban nemi ka rike mini yara ba. Haka zalika ma ban nemi matarka ta ri'ke mini yarana ba. A ba ni kayana mana dole ne, zan iya rikesu mu rayu cikin nutsuwa da kwanciyar hankali."

"To ni kuma muddin a karkashin ikona ki ke yaran nan babu inda za su je muna tare har abada, tunda ina tare dake ni ba zan iya rabuwa dake ba."
Na dube shi ina gyada kaina na ce." Haka ka ce ko?''
"Kwarai kuwa, haka na ce, sai ki yi duk abinda za ki yi tunda ke ba za ki rarrasu ba.
"Zan kuwa yi, ai ba kai ka haifar mini su, baka da wani ji'bi dasu don haka baka da hujjar da zakace dole sai ka rikesu anan zan nuna maka karfin ikona."

Ya ce." Sai ki nuna din ina jiranki..'' Daga haka ya cika ni tare da jan tsaki ya juya ya fita yana fad'in." Sakarai kawai kullum kina girma kina cin tasono."
Silalewa na yi a k'asan d'akin na yi zaman dirshan na dinga tikar kuka. An dake ni an hana ni kuka kuma an bi ni da bakar magana. Wace irin masifa ce wannan mutum bai haifi yara ba ya ce lallai sai ya rike su.
Ina cikin wannan yanayin Hauwa ta shigo sanye da hijabi a jikinta idonta jawur! Na tashi tsaye da sauri Ina kallonta gabana na fad'uwa. Minal ta dire mini a gabana tana fad'in.'' Ga takwararki nan Amina ubanta ya ce na tafi gidanmu."
Cikin kad'uwa da muguwar fargaba na ce." Ki tafi gidanku akan wane dalili Hauwa?"
"Saboda na gaya miki abinda yake faruwa." Ta fad'a tana juyawa da niyyar fita. Na bita da sauri yayin da Minal din ta tawo kataf katafi ta rike gefan hijabinta tana kuka. Na ce." Shine kuma ke sai ki tafi."
"To dama ai kamar akan 'kaya nake wallahi na gaya miki a gajiye nake." Na ce." Ita Minal din mai tayi miki to?"
"Cewa ya yi na ajiye masa yarinya."
Wani takaici ya yun'kuro mini lallai Alhaji Amadu ya mutu ya bar baya da k'ura. Iyalinsa na nema su tarwatsawa aminin nasa rayuwa. Na tabbatar da cewa ba kowane ya janyo wannan hayaniyar ba sai Salim.
Na ce." Yana ina maigidan?"
"Shi ya sani.'' Ta fad'a a takaice tare da sake nufar hanyar fita. Na ri'ke hannunta ina fad'in." Babu fa inda za ki je Hauwa."
Dariya ta yi irin ta takaici ta ce." Ai ba ke ki ke aurena ba Amina, maigida ya ce na fitar masa daga gida zaman me zan yi."
Jan hannunta na yi muka zauna kan gado na dau'ki Minal na d'ora mata a cinyarta sannan na d'auki wayata. Kiransa na yi bugun farko ya d'aga kamar yana jira.

Littafin nan na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na ce." Yanzu kai don girman Allah ba ka ji kunya ba, tsofai tsofai da kai kake aikata irin abun yara?"
"Mai na yi kuma? Ke ba kya jin nauyin furta mini maganar da duk ranki ya so ko Amina?''
Na ce." Hauwa dai ko babu aure tana da 'yancin zama na dindindin a gidanka, to balle bayan wannan alakar akwai ta aure da zuria a tsakaninku, da ka ce ta tafi gida kai ba ka ji nauyi ba?"
"Bata da wani 'yancin zama a gidana sai na so, tunda ba ta ji nauyin shure maganata ba, ni ma babu wani nauyinta da zan ji, kuma ina ruwanki matarki ce?"
'Dan sassautawa na yi domin kuwa ba zan so a ce dalilina sun samu matsala ba. Na ce." Idan saboda ta gaya mini wannan maganar nan ya sanya har ka yanke mata wannan hukuncin ka yi hakuri ka ji."

Shiru ya yi bai ce uffan ba. Na ce." Ka janye abinda ka kudirta akanta domin kuwa sam bai dace ba."
"Kin yarda ta yi ba daidai ba yanzu?"
Shiru na yi ban ce komai ba. Ya sake maimaita maganarsa nan ma ban ce masa komai ba. Ya ce." To tunda bakinku daya kin ga kuwa babu amfanin zama da macan da bata buk'atar zaman lafiya da kwanciyar hankali. Hauwa kawai ta tafi gidansu kafin na gama yanke hukunci ta san matsayinta, tunda har za ki iya d'aukar fillo ki toshe mini hanci don na mutu ai lamarin babban ne a wurina Hauwa ta samu nasarar tayar mini da husuma ni kuma zan d'auki matakin da ya dace a kanta."
Gwiwa a sanyaye na kashe wayar ina kallonta babu damuwa a tare da ita tace." Ai na gaya miki Amina mutumin nan kaf dabi'unsa sun canza muddin akan lamarin matarsa ne yakan iya cin mutuncin kowa."
Na ce." Babu da inda za ki je." Ta yi shiru tana kallona ina laluban wayar Hajja bugu daya ta daga. Cikin rawar murya na gaisheta ta amsa tana fad'in duk kuna nan lafiya ko Amina."
Na ce." Lafiya lau Hajja don Allah ki yi masa magana matsala suka samu da Hauwa shine ya ce wai ta tafi gida."
cike da mamaki ta furta." Hauwa ta tafi gida akan wane dalili?"
Shiru na yi ban ce komai ba.
Cike da kulawa ta ce." Amina ki gaya mini menene yake faruwa kin ji ko kada ki rufe mini komai.''
Hawaye suka silalo mini na ce." Hajja Hauwa ba ta yi masa komai ba wallahi, asalima ma matsalar ni ta shafa saboda kawai ta gaya masa gaskiya shikkenan yake jin haushinta."
Ta ce." To gaya mini wace matsala ce, ni zan yi maganinta, Hauwa kuma ki gaya mata kada ta fito."
"In sha Allah, gata nan a kusa da ni, na hana ta fitowa."
"To hakan ya yi ina saurararanki." Tafad'a cikin nuna damuwa. A nutse na fara gaya mata tun daga farko abinda yake faruwa har zuwa yanzu da ake wannan rikicin.

Hajja ta jima cikin alhini da takaici kafin ta ce." Ki yi hakuri a matsayinki na babba kuma uwa. Amina tabbas ko ba ki fad'a ba nasan idan za a tona zuciyarki to tanan cikin kunci da b'acin ran wannan lamari. Ki jure lallai kuma ya zama dole a yi wa tufkar hanci saboda gudun abinda zai afku anan gaba na rashin dadi. Zan nemi shi zai kuma zo nan inda nake akan maganar nan domin ni kaina ban yarda da hakan ba. Sannan duk abinda zai yi muku kada ku saurareshi. Ki jadaddawa Hauwa cewa da yawuna ban amince ta fito ba. Ke kuma ki yi hakuri kin ji ko, nasan abinda da ciwo a zucci amma in sha Allahu gaskiya za ta bayyana kanta.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta

Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*87*
Muryar Masa'udu ta katse tunanin da nake yi. na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." Kai mu jabi park."
Cike da bin umarni ya ce." An gama.
Motar ta yi shiru ni da yaran duka muna cike da zullumi mussaman Yusi da nake hankalce dashi yana goge hawaye a fakaice. Ban tsawatar masa ba

domin kuwa ban san mai yake ji a zuciyarsa ba, amma zahiri wannan shine iya gatan da nake ganin zan yi musu a duniya. Ba zai yiwu a ce koyaushe rayuwarsu ta kasance cikin kyara da hantara ba. Sun fara kaiwa munzali na girma a wannan lokacin ya kamata ace mun had'u ni dasu mun gina gobe dalili watarana za su yi aure su tara iyali suma. Sannan zuciyata ba za ta iya cigaba da jurar ganinsu cikin kaskanci ba, arziki Allah ne yake bayarwa su fita su nema kowa ya tsaya da k'afafunsa.
Cikin ikon Allah motar dana sanya su ta yi lodi saura bai fi mutum hud'u ba. Cike da dauriya da ko'karin kara musu kwarin gwiwa muka yi sallama na ce lallai idan sun sauka Kamalu ya kira ni tunda da waya a hannunsu.
Ban gushe daga wurin ba har sai da na tabbatar da tashin motarsu sannan na sauke ajiyar zuciya na gyara zaman nikab din da yake fuskata tunda ban fito ba sai da na sunkufe jikina ta ko'ina dalili ba na so a gane wata ala'ka da za a yi yamadidi da ni, kuma safiya ce tashar babu wadatar mutane da yawa sosai.
Kai tsaye na nufi wajan da Masa'udu ya ajiye mota.
Yana ganina ya taso daga inda yake ya bud'e mini na shiga na zauna sai a lokacin na ji wasu gagariman hawaye masu radad'i sun k'wace mini. Wato ni kuma haka kaddarata take, ina ro'kon Allah Ya ba ni ikon cinyeta ya kuma saukakawa yaran nan rayuwa ya basu hakurin maraici.
Ina komawa gidan na samu Hauwa da Momi zaune a falo, amma babu cikakkiyar sakewa a tsakaninsu Hauwa ta yi zaman gadara da ki ce kule na ce miki cass domin kuwa fuskarta tamkar kunun tsamiyar da ya kwana a rufe. Kusan a tare suka amsa sallamata.
Kwarai da gaske na yi kokarin danne abinda nake ji a zuciyata game da al'amuran dake faruwa. Na nemi wuri na zauna babu yabo babu fallasa nake kallonta ina sake nazari akan al'amuranta. Ta tsuke sosai ta yi fayau abinka da mara jiki da gasken ne bata da lafiyar domin alamu sun nuna babu wani kuzari da karsashi a tare da ita.
Ita ta fara gaishe ni a tsanake na amsa ido na a kanta ina sauraran abinda take tafe dashi ta gyara zamanta kad'an tana kallona sai ta sauke ajiyar zuciya a hankali
Ta ce." Amina na shigo nan ne saboda ke domin mu tattauna abubuwan dake faruwa da yaranmu, Allah Ya ga zuciyata ban shigo cikin rayuwarku da wata niyya ta cutarwa ba, kuma ban had'a kai da Salim domin ya ci mutuncin Kamalu ba, asali ma abinda yake aikatawa ba ni da masaniya sai bayan ya aikata din nake samun labarin." Ta yi shiru tana sauke ajiyar zuciya a karo na biyu kafin ta cigaba da cewa."
Yana da kyau a matsayinki na uwa mai hankali ki yi nazari mai kyau Amina idan hankali ya 'bata fa nutsuwa da dattako ake sanyawa domin nemansa bai kamata ace kin d'auki munanan shawarwarin da ba za su zama silar gyar........Hauwa ta katse ta cikin fusata." tana fad'in "Ai dama ban ce kin shigo gidan nan domin ni ba Maryam, ko kuma kin ji na ce miki kin shigo ne da mummunar niyya. Kin tsargu ashe ai shi mara gaskiya dama kullum cikin zullumi Hajajju ki dube ni da kyau ki ga ni, a waye nake k'warai babu wata kinaya da za ki yi mini kafin ki san Amina da yaranta ni na santa na kuma

zauna da ita. Idan har mijinki ya gaya miki cewa da hannuna wurin matakin da Kamalu ya d'auka bai yi miki k'arya ba, ga ni a zaune ai ina jiran hukunci tunda ku kun iya take gaskiya da gangan."
Cikin rashin sukuni na ce." Hauwa menene don Allah, duk cikinmu nan babu yaro karami tunda har ta shigo domin mu tattauna magana dan samun daidaito bai kamata wasu maganganu mara dad'i su biyo baya ba kuma."

Ta ja dogon tsaki tana fadin
"Kina jin irin jirwayen da take yi mini ai, ai mu 'yan iska ne marasa 'yancin kai tunda mijinta haka ya nuna mata ba mu da mutunci da kima sannan ba mu da sirri komai muka yi a tambad'e ita nata sirri koyaushe cikin danda'be shi yake baya so kowa ya ji. Bazan jure d'aukar cin kashi daga 'bangaranta ba wallahi tallahi."
A nutse ta ce." Ba halina ba ne raina mutum Hauwa, kuma kamar yadda ki ke hasashe hakane maigidan ya gaya mini komai ke ce ki ke ko'karin ganin lallai sai an yi 'batacciya domin kuwa abinda muke ta bunnewa dalilin gudun rikici mai muni ke ki ka gayawa mahafiyar yaron nan, kuma ki ka cire nauyi da kunya ki ka dubi tsabar idon yaron nan Kamalu ki ka gaya masa to kin fad'a kin ji dadi kuma in sha Allahu abinda ki ke fata ba zai faru ba da izinin Allah."

Hauwa ta mike tsaye tana huci ta ce." Kin yarda yaronki mahassadi ne, kuma sharri ya yi wa Kamalu ko ba ki yarda ba, ke yanzu don girman Allah ba ki ji kunya da nauyi ba
ai ita karya fure take bata 'ya'ya wallahi ni dai Hauwa Maryam ba ki isa ki siye ni da kudi da abin duniya ba. Wannan gingimeman sharri da d'anki ya alak'anta marayan Allah dashi saboda rashin adalci da son zuciyarku sai ku ja baki ku yi shiru babu wani mataki da ku ka d'auka. Sannan kuce ba za a yi magana ba, to ni na sayi rikicin don girman Allah ki d'auki mataki a kaina. Kenan wannan ya nuna kun sake bawa yaron lasisin ci gaba da aikata abinda yake yi dalili kun nuna masa akan daidai yake, ke da mijinki kun daure masa gindi saboda kun tara abin duniya kuna ganin kun fi karfin hukuma ko? to ku d'aukaka k'ara don Allah allura ce zata tono garma menene ba mu sa ni ba Maryam na fad'a din idan ta yi miki zafi ki kaini 'kara ko kisa tsinken tsire ki tsire ni!"

Na tashi tsaye da sauri
na tare ta tare da mayar da ita kan kujera na zaunar sai huci take yi tabbacin a fusace take kuma a shirye take da duk abinda zai faru.
Hayaniya ta fito da Baba Tabawa daga kicin tana fad'in." Mai yake faruwa ne don Allah ku yi aiki da hankali da girman shekarunku kada hayaniyarku ta d'auki hankalin yaranku k'ananu har su fahimci abinda yake faruwa, kun san dai yaro da ri'ke abu a zuciyarsa...

Littafin gudun aure na kudi ne, don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Cikin numfasawa Hauwa ta koma ta zauna tana huci! ita kuma Momi ta yi 'kasa da kanta k'walla cike a kwarmin idonta. Alamu sun nuna cewa ba ta iya fad'a na cacar baki ba koda fad'ansu ya yi tsayi da Hauwa ita za ta kaita kasa.
Har cikin zuciyata ban ji dad'in abinda ta yi mata ba duk da cewa duka su biyun ban san menene a cikin zuciyoyinsu ba don haka ba daidai ba ne abinda ta yi tsinka na k'asa da kai ma tozarci ne ballantana wanda yake sama da kai ashekaru. Ni da ita duka haihuwa ce ta janyo mana domin kuwa da yara ba su had'a ba ina ganin babu wani dalili da zai sanya na yi sa'insa da ita akan namijin da ba shi da wani tabbas. Tun farko itama Hauwan da ta d'auki shawarata abinda yake yi akan matarsa ba zai dameta ba tunda ta san tafi amfanarshi fiye da ita ko a wurin tarayya ta aure ne. Kuma ita ce uwar mai sunan mahaifinsa Ibrahim Khalil, uwa uba kuma 'yar uwarsa ta jini. Hauwa ba ta fi ni kishi ba wallahi kawai na fita ha'kuri da juriya ne dalilin gwagwarmayar da na yi a rayuwa ita ba ta yi irinta ba.
BabaTabawa ta koma kicin jikinta duk a sanyaye bayan cikin hikima irin ta manya ta yi mana nasiha aka ci sa'a kuma Hauwa bata k'alubalanceta ba.
Falon ya yi shiru bayan gushewar baba Tabawa daga wurin babu wanda ya sake magana. Ita Momi din tunda ta sunkuyar da kanta kasa ba ta sake d'agowa ba tabbatacin ta ji ciwon irin tijarar da Hauwa ta yi mata.
'Dagowar da za ta yi kuwa sai ya yi daidai da kwaranyowar ruwan hawaye a dakalin fuskarta. Ba ta yi yun'kurin gogewa ba sai ta kalleni ta fara magana cikin karaya da zullumi." Amina ni na haifi Salim amma wallahi ba na goyon bayansa akan irin abubuwan da yake aikatawa na rashin kyautatawa. sannan na sake jadadda miki babu yawuna ka haifi d'a ne kawai amma ba ka haifi halinsa b..... Hauwa ta yi saurin cewa." Kuka ai yanzu ki ka soma in sha Allahu rabbi Hajiya kina
fama da gagararan d'anki da ki ka kasa sarrafawa ina ke ina iya yi wa yaran wasu tarbiya wallahi ki ji tsoron Allah da Annabi, ga shi dai da bakin ki kin fad'a cewa Salim baya jin maganar ki, sannan nan Nusaiba ta shigo har gida ta yi mana rashin kunya, ina tarbiya anan kina so ki lalata mana yaranmu ne, ko kuma kina so su yi koyi da abinda yaranki suke yi duk a had'u a yi mutuwar kasko gabad'aya ko ba haka ba ne."
Shiru ta yi ba ta ce mata komai ba. Na dube Hauwa da ta kasa zaune a kan kujera sai zabura take yi kamar ta yi tsalle a gabanta ta rufe ta da duka.
Gyada kaina na yi ban ce komai ba na mayar da hankalina kanta domin sauraran abinda take cewa." Na nunawa Salim takaici da 'bacin raina na kuma gargade shi akan kada ya kuskura abu mafi muni ya sake faruwa irin haka. Ina kwance cikin ciwo jiya na samu labarin doki-in-doka da ya shiga tsakaninsu. Wannan shine abinda ya fi tayar mini da hankali na ce kina ina har hakan ta faru. Ban haifi Kamalu da Yusi ba, amma yau zan gaya miki wani abu da nake ji game da yaran nan a zuciyata wallahi ina sonsu fiye da yadda ki ke tsammani. Yadda nake jin yaranku gabad'aya a raina haka nake jin wanda na haifa. Ina rokonki da Allah da annabi kada ki yanke kyakykyawar ala'kar dake tsakaninmu. Kada ki yi yun'kurin datse k'akkarfan zumuncin da yake tsakanin Adamu da Yusuf domin kuwa d'azu Adam ya je

mini cikin damuwa  cewa kin tura  yaran  nan kano, ki yi hakuri yara su dawo mu cigaba da rayuwa cikin aminci na yi miki alkawari wani abu makamancin wannan ba zai sake faruwa ba. Kuma in sha Allahu Salim zai shigo ya baki ha'kuri komai ya shige da izinin Allah."

Ta gama maganar tana sanya hannu domin share hawayen da yake ta tsiyaya a fuskarta. A nutse na ce." Ki yi hakuri ki daina kuka akan wannan lamari Momi wallahi ban k'ullaceki ba, kuma ni har abada akan yara ba zan yi rigima dake ba, amma ina so ki sani ce wa muddin Kamalu da Salim na tare a Inuwa daya to sa'bani ba zai daina giftawa a tsakaninsu ba. Abinda ba na fatan ya sake faruwa. Ba wai ba ki isa ba ne, kin fi karfin komai a wurina domin ban mance alherinki ba, ki yi hakuri yara dai har abada sun bar nan in sha Allahu suna can hannun dangin Babansu sai dai su zo da ziyara. kuma ban isa na yanke zumuci da ala'ka ba tunda ai ba ni na had'a ba......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*85*
Babu wanda ya ce komai sakamakon saukowar maigidan daga sama ya canza kaya amma ga yanayin yadda fuskarsa ta ke a cude nasan duk ya ji maganganun da Kamalu yake furtawa.  Bai ce mana komai ba haka zalika bai kalli inda muke ba ya kama hanyar fita cike da tsananin b'acin rai a tare da shi.
Yusi da sauri shi ma ya  bi bayansa ba tare da ya yi wa kowa sallama ba.
Hauwa ta ja tsaki tana fad'in." Haba ai ni yau kwanan farinciki zan yi wallahi, irin wannan mutanan rashin mutunci da tijara shine daidai da abinda ya kamata da su."

Muka yi shiru babu wanda ya tanka mata. Ta dubi Kamalu da har yanzu yake huci yana numfarfashi.
A nutse ta ce." Kada ka wani damu  Kamalu abinda ka yi shine daidai domin idan har da ni da uwarka za mu zauna mu zuba ido akan abin nan to wallahi tallahi babu wani mataki da uban rikonka zai  d'auka. Abinda ka aikata a yanzu shine ya tabbatar mini da cewa kai dan halak ne ka haifu kuma kana kishin kanka, sannan kuma ya nuna cewa Salim sharri ya yi maka baka aikata ba, kada ka sare ko ka tsorata don suna da kud'i wallahi ba za su yi nasara a kanka ba.

Idan har Salim da uwarsa sun ce za su bi kadin jinin da ka zubar masa ni zan biya su zan kuma shige maka gaba tsayuwa gaban alkali masifa yanzu aka fara wallahi."
Na jima ina kallonta tare da yin nazari a kan maganganunta. Yadda ta d'aukaki lamarin take sake zuzuta shi shine abinda yake sanya ni tunani. Ita da Momi din duka na kasa gane inda suka sa gaba. Masifa yanzu aka fara. Wannan maganar tata ita nake ta nanatawa a cikin raina. Tabbas k'azafin da Salim ya yi  wa Kamalu mai muni ne sosai, to amma ni ban shirya tsayuwa gaban alkali akan hakan ba. Kamalu dai duk da ba a shedar mutumin yau ina da tabbacin bai aikata ba. Ba ni son bala'in ya yi tsayi domin shaidan ya samu mafaka.
 Tunda ni da yaro mun tauna tsakuwa shikkenan nasan duk daran dadewa gaskiya zata bayyana. Ba zan tsaya da ita domin yin shari'a akan yara ba, ba kuma zan ce mata komai ba domin bata isa ba, mijinta da ya daure mata gindi shine daidai da ni. Sai dai yadda Hauwa take zafafa lamarin da ko'karin sake rura wutar rikicin shine na kasa gane azancinta na yin hakan shin soyayya ce ko kuma da wata manufa a zuciyarta. Ba ni so akan abinda ya shafe ni auranta ya samu tangard'a amma na lura ita ba wannan ne abinda ya dame ta ba. Tunda har na riga na yanke hukunci na kuma gaya mata ya kamata ace itama ta sassauta saboda gudun afkuwar abinda zai sanyata ta shiga nadama tare da danasani.

Yusi ya sake dawowa a karo na biyu daga bakin kofa ya tsaya yana fad'in." Ka zo in ji Momi."
Hauwa ta kalle shi sama da kasa kafin ta ja tsaki ba ta ce  dai komai ba. Sai harara da ta ke wurga masa. Ya sake maimaita maganarsa "Momi ta ce ka zo."
Ya ce." Ka je ka ce mata gani nan."
Har ya juya zai fita na ce." Yusi zo nan." Ya juyo yana kallona na ce." Zo."
ya zo ya durkusa kusa da ni.
Na ce."Ka za'bi Momi ko?" Ya yi shiru bai ce mini komai ba.
Cikin tsawa na sake cewa." Momi ce uwarka ba ni  ba ko Yusi?"
Sai ya sa kuka yana cewa." Mama don Allah kada b'acin rai ya sanya ku yi abinda zai janyo muku nadama, Momi duk abin nan da yake faruwa wallahi ba ta da laifi, tana sonmu dukanmu na yarda Yaya Salim ya yi laifi amma kada abin ya shafeta itama cike take da takaici da b'acin rai."
Hauwa ta ce." Idan abin ya dameta tunda farko mai yasa ba ta shigo an tattauna ba." Da sauri ya ce." Bata da lafiya wallahi, shiyasa bata shigo ba a kwance take."

Yana rufe baki Nusaiba ta shigo da tawagar yaranmu a bayanta ta ci kuka ta k'oshi domin kuwa fuskarta har ta d'an tasa idonta ya yi ja wata'kila d'an uwan ne ya kira ta a waya a gaya mata. Yaranmu kaf tun daga kan Khalil Hassana da Usaina Minal suna bayanta.
Ba tare da ta gaishe da kowa ba tana daga tsaye take ce wa." Mun gode bisa abinda aka yi mana, Allah Ya saka da alheri, mu ba mu gaji fitina da tashin

hankali ba domin tarbiyar da iyayenmu suka yi mana kenan, koyaushe Mominmu cikin yi mana nasihar mu zauna lafiya da kowa take yi. Mahaifinmu kafin ya rasu k'arshen maganarsa shine mu ri'ke Babanmu Alhaji Tajo a matsayin uba. Wannan dalilin ya sanya ba za mu yi fad'a daku ba domin muna kallonsa a matsayin ubanmu, kuma Shima ya rike mu a matsayin 'ya'yansa. Bayan haka kuma muna buk'atar nutsuwa kwanciyar hankalinsa, shine dalilin da ya sanya Mominmu tace mu yi hakuri. "
Ta sauke ajiyar zuciya kafin ta cigaba da ce wa."
Sannan yaranku ga su nan Momi ba ta da lafiya, dama kokari ne kawai irin nata ni kuma na ce kowacce ta raini abinta."
Da sauri Hauwa ta ce." Sannu uwar iya, sarkin kitifi da makirci 'yar na gada idan ba ki yi ba ai baki sha nonon uwarki ba, mu so muke mu kwantar da uban rik'on naki ciwo ya kama shi shiyasa muka hana shi sukuni. Wato ke baki ga abinda dan'uwanki ya aikata ba ko har kina da bakin magana saboda ba ki da kunya ko.
Yara dama ai ba mu muka sanyata ta ri'ke ba, ita taga zata iya, mu ai taimakonmu ki ka yi da ki ka dawo mana da su dama fin karfinmu aka yi, rashin lafiya kuwa kowa ma a cikinta yake mara kunyar k'arya sakarai, wannan tabarmar kunya ki ke nad'ewa da hauka. Wanene musababbi idan ba d'an'uwan naki ba. Shi za ki jawa kunne a matsayinki na wadda take gaba da shi, cikinmu dai babu sa'arki da za ki zo ki yi wa d'ibar albarka, sai me dan yara sun dawo gidan ubansu dama ai ita ta nema ni da Amina dai babu wadda take da sha'awar barin yaronta a hannun uwarki."

Nusaiba cikin rawar murya ta furta." Kin ga ni ba sanya ki a cikin maganata ba, ko dana shigo kin ji na ambaci sunanki, wai shin ma ina ruwanki ne naga ai ba ke ce ki ka haifi yaron ba da har ki ke fuffuka duk fa abinda ki ka ji da shi wallahi daidai nake dake, ai dama an ce ke ce ki ka rura wutar ba kowa ba."
Hauwa ta zabura da sauri ta tashi tsaye tana fad'in." Ubanki zan ci la'ada waje don uwar uwarki ita data turo ki itace sa'ar yi na, duk wanda ya gaya miki ni nake turara wutar bai yi karya ba da gaske ni ce kuma sai na rurata ta ruru! ta cinyenku matsiyata masu kisan mummk'e."
Sai ta fashe da kuka mai karfin gaske ta sanya hannu ta toshe bakinta. Hauwa kuwa ko a jikinta. Na tashi na je na zaunar da ita ina fad'in." Menene haka Hauwa yarinyar nan ba sa'arki ba ce kamar yadda ki ka fada me yasa za ki biye mata."
Tsaki ta ja da k'arfi tana fad'in." Iskancin banza da wofi wai har wani fadi take yi an zalincesu su ba suga zalinci da suka yi ba kenan, ko shi wannan din ba mutum ba ne?" Ta fad'a tana nuna Kamalu dake zaune a kan kujera. Na ce." Ya dai isa abar maganar don Allah."

Ta yi shiru ba ta sake magana ba sai tsaki take ja. Ina juyawa ita kuma Nusaiban ta kama hanyar fita jikinta duk a sabule. Sai kuka take yi 'kasa-kasa tana jan hanci.

Ban ce komai ba na koma saman kujera na zauna kaina na sarawa tsabar tunani da zullumi.
Duk da abinda suka yi wa Kamalu sai da na d'an ji wani iri a zuciyata. Gabad'aya ma yaran ba su iya fad'a ba daga ita har Salim din domin kuwa da sun iya fad'a ina ga da ba su fara ko'karin neman sulhu ba shi karamin cikinsu ma Adam kenan tunda ake hatsaniyar bai ce komai ba sai dai kuka da share hawaye da tissue shine kadai abinda yake yi gwara Yusi ya zo yana kalubalantar d'an uwan nasa.
Da zai tafi kiran da Momin take yi masa ban hana shi ba, amma hukuncin da na yanke a zuciyata yana nan ban janye shi ba sai yaran sun bar gidanta da garin ma gabad'aya domin kuwa ba zan iya ba da wannan masifa ba na shirya tarar kowane irin kalubale.

Washe gari da safe Kamalu 'kalau ya shigo mini tsaf dashi cikin Pakistani yana ta kamshin turaransa da ya riga ya zauna masa a jiki
. Muka gaisa da yake a d'aki ya same ni ban kai ga fita falo ba tukkuna na ce masa ya je ya gaishe da Hauwa da Baba Tabawa ya dawo. Ya fita minti biyar ya dawo ya zauna a gefena. Na dube shi a tsanake na ce." Jiya mun gama magana da Hamusu a waya zan sanyaku a motar haya zuwa kano sai ku dinga waya dashi kafin ku sauka. "
Ya ce." Na ji dadin hakan Mama, kin ga kuma Baba bai jima da tafiya kanon ba don har d'akinmu ya same mu ni da Yusi yana tambayarmu zai je kano ko muna da sa'ko wurin Baba Hamusu.

Littafin nan na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Shiru na yi ina d'an nazari tafiyarsa kano da gaggawa irin haka tana da ala'ka da kiran Hajja dama ta ce zata kira shi babu tamtama kuwa wurinta ya tafi.
Na ce. " Hakan ya yi daidai ni ma na ji dad'i, ka je ka kira mini Yusi amma kada ka gaya masa komai."
Ya ce." To shikkenan. Ya tashi ya fita da sauri. Ni kuma cikin gaggawa na shiga toilet domin yin wanka. Ina fitowa su Hassana suka shigo tsaf gabad'ayansu Baba Tabawa ta shiryasu. Na ce." Kun zo mu gaisa ne, ashe kun san ni?"
Husaina dariya ta kama yi ta haye gado ta kwanta tare da sanya babban yatsanta a baki tana totsa.
Na ce." Ke ba ki daina tsotsar hannun nan ba dama." Ta yi shiru ba ta ce mini komai ba sai ma ta janyo rigar baccina da na cire da yake mai laushi ce ta dinga shafa rigar da hannunta.
Hassana ta je ta cire hannun daga bakinta cikin tsamin baki ta ce." Momi fa ta hana ki."
Na dube su Hassanar na cire hannun ita kuma Husainar na mayarwa bakinta. Na juya da niyyar bude wardrobe na d'auko kaya na ji kuka da k'arfi da sauri na dube su. Husaina ce ke kuka sosai ta cukume Hassana da kokawa Minal na gefe a tsaye tana kallonsu.

Wajan na nufa ina fad'in." Mai ya had'aku." Cikin tsamin bakinta tana kuka ta ce." Dutana ta yi, ina luwanta da ni."
Dariya nasa na ce." Ke Hassana mai yasa ki ka duteta?"
"Momi ta hanata tsotsar hannu." Ta ba ni amsa tana zum'bura baki.
Kamulu ya shigo ya ce." Fad'a suke yi ko Mama." Na ce." E dama haka suke yi a gidan Momin"
"Wallahi yini suke yi fad'a ai Mairo tana aiki kuma Hassana ce mai zalinci. Wataran Momi idan ta gaji dai sai ta cewa da Mairo ta goya Husaina don a samu mafita nan sai ta ce ba ta yarda ba ta dira kuka. Momin da kanta take cewa a d'auko mata zani sai ta goyata ake samun zaman lafiya."

Na ce." Momin da kanta take goyo." Yana 'yar dariya ya ce." E, ai rigimar Hassana tana da yawa fa wasu lukutan Momin ce take iya sarrafata ga gaddama da rashin yarda da mutane."
Na gyada kaina ban ce komai ba, zuciyata ta shiga zullumi da tunanin inda matar nan ta sa gaba akaina da yarana.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri

Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*86*
"Ina Yusi din yake?" Na tambaye shi ba tare da na dube shi ba.
"Gashinan zuwa, amma mama kin san ba lallai ne ya shigo shi kadai ba duk inda ya ajiye kafarsa anan Adam yake ajiye tasa. Ya ba ni amsa da dan sanyin jiki.
Shiru kawai na yi ina nazari, Adam dai ko mayya ce ta haife shi dole su rabu domin kuwa
 babu  wani dalili da a yanzu zai hana yaran nan barin garin nan.  Na ce." Je ka falo, idan sun shigo tare ka turo mini shi." Ya amsa da "to shikkenan. Kafin ya sanya yaran a gaba suka fita.
Gama sanya kayana ke da wuya Yusi ya shigo ya sha ado cikin yadin kufta d'inkin kansa abin kallo ne ballantana takalmin da yake kafarsa. Babu shakka matar nan ta na hidima da  yaran  nan kuma duk abinda za ta yi babu bambanci abinda Adamu zai sanya a jikinsa shi Yusi zai sanya duk tsadarsa kuwa. Ko turarukan da suke amfani da shi wallahi sai mai karfin jari. Jikina ya yi sanyi kalau a yayin da nake duban yaron cikin Kamala da nutsuwa tare da kwarjini fatarsa luwai alamar hutu da jin dad'i sun ratsa jikinsa.
Kafin ya zauna a gefana sai da ya d'an risina tare da furta." Mama ina kwana, an tashi lafiya?"
Na amsa a nutse ina sake nazartarsa har yanzu babu walwala da sukuni a tare dashi tabbacin abubuwan da suke faruwa na damunsa. Ya nisa kafin ya sake fad'in." Momi ta ce tana gaisheki ta ce na gaya miki za ta shigo idan an jima."
Sai da nutsu sosai na dube shi babu fara'a a tare da ni na ce." Yusi ina so ka bud'e kunnuwanka da kyau ka ji abinda zan gaya maka, hukuncin na yanke kuma babu mahalukin da ya isa a wannan ga'bar da tura ta kai bango ya dakatar da ni." Na yi shiru Ina kallonsa yayin da gabad'aya ya shiga nutsuwarsa alamun fargaba da tashin hankali sun gama bayyana a fuskarsa.
Na cigaba da ce wa." Hukunci na yanke akanka kai da d'an'uwanka Kamalu za ku bar garin nan gabad'aya rikonku zai koma hannun Hamusu za ku

cigaba da ri'ke mini harkokina yanzu shirin da na yi kenan domin tun jiya na gayawa Hamusu halin da ake ciki saboda haka yanzu za mu je tasha tare na sanyaku a mota in sha Allahu rabbi."

Matsananciyar damuwa ya shiga wadda baki ba zai iya misalta irinta ba. Ina kallonsa yana ta ko'karin mayar da hawayen da ya cika kwarmin idonsa amma duk dubararsa sai da ruwan hawayen ya kwaranyo kumatunsa. Murya na rawa ya ce." Mama mai yasa za ki yanke wannan hukuncin, ki dubi Allah da Annabi ki janye kada ki hukuntani akan laifin da ba nawa ba. Ki dubi k'auna da soyayyar da Momi take yi wa jininki kada ki sanya 'yan uwanta su yi mata dariya. Mama ni da Adam akwai k'auna da sha'kuwa sannan ba na so na rabu da Baba, ba zan ta'ba mantawa da hallacinsa a gare ni ba. Sannan Momi tana nan tana yi mana shirye shiryen tafiya karatu saudiya makarantar da Yaya Salim ya yi karatu, ki yi hakuri Mama, kada ki hukunta Momi da laifin da itama ranta yake soyuwa."
Ga'bo'bina ne suka yi sanyi ganin yadda hawaye suke zarya a dakalin fuskarsa. Ya kama hannuna ya ri'ke kamatau jikinsa har karkwarwa yake yi.
Na ce." Yusi ba ka ji wani iri a cikin ranka ba a lokacin da Salim yake yi wa dan'uwanka sharri, abu mafi muni fa ya jingina masa. Da farko ban d'auka abin ya yi tsanani ba na danni zuciyata duk domin a zauna lafiya. Amma Yusi ba abu ne mai wahala ba a yanzu dai na tsaya da Momi da Salim a gaban alkali domin yin shari'a dasu akan wannan mummunan sharrin da Ubangiji ya halakar da wani gari kacokan akan aikatawa. Sai dai na yi hakuri ne bisa abinda uwar rikon naku take aikatawa a kanku na alheri wanda idanu suke gani sanin bad'ini kuma sai Allah. Wannan shine dalilin da ya sanya ni tausar zuciyata akan danne maganar ba tare da na d'auki matakin  kare hakkin Kamalu ba. Allah shahidi ne zai bayyana gaskiya da gaggawa. Yusi kana maganar  ba za ka iya rabuwa da Baba  ba shin zaka iya tuna ubanka Yaya Aminu? ko ka manta dashi ne tunda yanzu ka kasance cikin daula wurin iyayen rikonka har kake ko'karin canza shi a matsayin wanda ya zama 'kashin bayan samar da kai!"
Na yi shiru Ina mayar da hawayen dake ta yun'kurin zuba.
Shi kam kuka yake yi sosai. Cikin rawar murya na ce." Nasan ka manta da shi ko Yusi, ni da nake raye a duniyar ma ka manta da ni to balle babanka wata'kila jin dadi ya sanya ba ka yi masa addu'a tunda ka nunawa duniya ka yi sabbin iyaye."
Hawayen da nake dannewa suka goce da karfinsu duka dinga fafara gudu a kumatuna. Na ri'ke hannunsa da kyau na ce." Ka ture maganar sabo da hallaci da kyautatawa Yusi duka nasan mutanan nan biyu sun yi mini ko da ba don Allah suka yi ba to  ni ma ina rokon Allah ya ba ni ikon rama musu, amma ba na ji a zuciyata za a samu zaman lafiya da juna muddin Kamalu da Salim suna zaune inuwa daya kuma a makwanci d'aya. Kun girma da kai dashi ku tafi ku taimakawa kanin babanku ku nemi arziki ta hanyar halak, ina da shaguna da dukiya a hannun Hamusu sai mu 'bullo da hanyoyin nema domin mu gina kanmu da gobenmu, watarana za ku yi aure, za ku hayayyafa

a wannan lokacin ya kamata ace kun dogara da kanku Yusi ba wai a ce koyaushe kuna ra'be-ra'be a gidajen mutane ba."
Kuka kashir'ban yake yi yana fad'in." Mama na fahimci azancin ki, na gane abinda ki ke so na gane, amma don Allah Ina neman alfarma a wajanki duk rintsi kada  ki yi rigima da Momi wallahi mutuniyar kirki ce, ina kaunarta kamar yadda nake kaunarki Mama, kuma duk abin nan da yake faruwa babu sanya hannunta ko da anti Nusaiba ta dawo muku da yaran nan wallahi bata sani ba lokacin tana bacci da ta tashi ta samu labari wallahi sai da ran anti Nusaiba ya 'baci da kuka ta bar gidan. Ita kanta Momi ta rasa yadda za ta yi da su. Adam ne kawai bai shiga rigimar ba, Yaya Salim da anti Nusaiba sun had'e kansu sun daina jin maganar Momi."
Na ce." Sai ka ce mara hankali Yusi, ba zan yi rigima da ita ba, to akan me? ai ta yi mini alheri, abinda dai nake so da kai shine ka samu nutsuwa ka kuma kwantar da hankalinka, maganar cigaba da karatu kuma ko ba ku fita waje ba sai ku d'ora a bayaro university ku kai matakin da kuke buk'ata in sha Allahu."
Ya rike hannuna yana kuka." Mama zan bi umarninki zan yi abinda kike so muddin hakan zai sanya ki daina wannan kukan. Jin dadi bai sa na mantaku a matsayin iyayena ba. Babanmu duk lokacin da na yi sallah ina yi masa addu'a, ban manta daku ba Mama, ni dan halak ne ban mance wahalar rayuwar da ki ka sha a kanmu ba. Har abada ba zan canza ku ba."
Na sunkuyar da kaina kasa ina tsiyayar da hawaye masu zafi da 'kuna. Gabad'aya duniyar ta gama fita daga raina saboda masifa da tashin hankali.
Tsaf ya goge mini hawayen idona yana fad'in." Ki yi hakuri Mama ki daina yi mana kuka don Allah."
Ban ce komai ba na tashi tsaye shima ya tashi tare da dafa kafadata da hannunsa.

Lokacin da muka fito falo Kamalu da Adam ne a zaune suna magana da sauri yaron ya zame daga kan kujerar da yake zauna yana fad'in."Mama ina kwana mun tashi lafiya?"
A nutse na amsa da kulawa sai ya koma saman kujerar ya zauna jikinsa duk a sanyaye. Hauwa ta fito daga d'aki da tawagar yaran a bayanta tana fad'in." Kun shirya kenan?" Kafin na amsa Adam ya gaisheta  ba tare da ta dube shi ba ta amsa kamar ba ta so. Na gyada kaina tare da kallon kamalu da kansa yake sunkuye na ce." Tashi mu tafi."
Baba Tabawa ta fito daga kicin hannuntà ri'ke da madaidaicin baho da dabino a ciki. A nutse muka gaisa kafin na d'ora da fad'in." Baba zan kai yaran nan tasha zuwa kano yanzu zan dawo in sha Allahu."
Ta ce." To shikkenan sai kin dawo Kamalu a gaishe da mini da Gwaggo da kyau sai kun dawo Yusuf." Yadda take magana shi ya sake tabbatar mini da cewa ba ta fahimci nufina ba domin kuwa da ta gane hukuncin da na yanke sai ta yi magana akan hakan.
Adam da sanyi jiki ya dubi Yusi yana cewa." Za ku je kano amma babu labari Yusi babu neman rakiya, ni ma ina so na je na gaisa da Gwaggo da Baba Hamusu."

Yusi ya riko hannunsa ya tashi tsaye muryarsa sanyi kalau ya ce." Wallahi ban san da tafiyar ba sai yanzu ka yi hakuri d'an uwa, idan har za ka je sai mu je ai babu damuwa."
Da farinciki a fuskarsa ya furta " Zan je mana bari na sanar da Momi kai kun yi sallama ko?"
Yusi ya girgiza kansa a hankali ya ce." Zan shigo yanzu na yi mata sallama.
Adam na fita ni ma na kama hanyar fita zuciyata cike da zullumi da nazari nasan ba karamin gagarimin rikici ne zai 'balle a gidan ba dalilin wannan matakin da na d'auka. Amma a shirye nake da tarar komai daga maigidan koda kuwa ta rabuwa ce. Ai an yi abinda aka yi, Allah Ya shige mini gaba.
Muna fita harabar gidan Masa'udu shine babban direbanmu da ya ajiye mana domin zurga-zurga dukda ba kasafai muke fita ba amma tun farko dama ya hana mu tu'ka mota a wasu lukutan ma ya gwammace shi da kansa ya ja akan wata daga cikinmu ta ja
Ya taso da sauri tare da risinawa yana gaishe ni na amsa a gurguje domin ba na so Adam ya sake shigowa ya same mu ban san mai zan ce masa ba.
Cike da girmamawa ya ce." Hajiya za a fito da mota ne?"
Kaina na girgiza a takaice na ce." A a.'' Ya biyo bayanmu da sauri Yana fad'in." Hajiya ki yi hakuri na kai ku don Allah" Ya k'arasa maganar a raunane.
Na Dan dube shi sai ya ba ni tausayi sosai suke ko'karin ganin sun ri'ke aikinsu sam ba sa son abinda zai 'batawa ogonsu rai ko su sa'ba umarninsa.
Na ce." Yi sauri to." Da dan gudu ya nufi wurin da motocin suke ya fito da daya da gaggawa har zuwa wurin da muke tsaye.
Kamalu ya bude mini na shiga na zauna kafin ya dubi Yusi cike da tsare gira ya ce." Malam shiga mota.'' Ya shiga ba tare da ya ce masa komai ba sai da akwai damuwa Mai yawa a tattare dashi don sai waige-waige yake yi.
Sai da muka hau titi sosai hankalina ya kwanta domin ni kaina ina jin nauyi da kunyar yaron ina kuma fargabar ya zo ya riskemu ba zan iya ce masa tafiyar ba zata yiwu dashi ba.
"Hajiya Ina muka nufa..... Muryar Masa'udu ta katse tunanin da nake yi.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN🖊*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*87*
Muryar Masa'udu ta katse tunanin da nake yi. na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." Kai mu jabi park."
Cike da bin umarni ya ce." An gama.
Motar ta yi shiru ni da yaran duka muna cike da zullumi mussaman Yusi da nake hankalce dashi yana goge hawaye a fakaice. Ban tsawatar masa ba domin kuwa ban san mai yake ji a zuciyarsa ba, amma zahiri wannan shine iya gatan da nake ganin zan yi musu a duniya. Ba zai yiwu a ce koyaushe rayuwarsu ta kasance cikin kyara da hantara ba. Sun fara kaiwa munzali na girma a wannan lokacin ya kamata ace mun had'u ni dasu mun gina gobe dalili watarana za su yi aure su tara iyali suma. Sannan zuciyata ba za ta iya cigaba da jurar ganinsu cikin kaskanci ba, arziki Allah ne yake bayarwa su fita su nema kowa ya tsaya da k'afafunsa.
Cikin ikon Allah motar dana sanya su ta yi lodi saura bai fi mutum hud'u ba. Cike da dauriya da ko'karin kara musu kwarin gwiwa muka yi sallama na ce lallai idan sun sauka Kamalu ya kira ni tunda da waya a hannunsu.

Ban gushe daga wurin ba har sai da na tabbatar da tashin motarsu sannan na sauke ajiyar zuciya na gyara zaman nikab din da yake fuskata tunda ban fito ba sai da na sunkufe jikina ta ko'ina dalili ba na so a gane wata ala'ka da za a yi yamadidi da ni, kuma safiya ce tashar babu wadatar mutane da yawa sosai.
Kai tsaye na nufi wajan da Masa'udu ya ajiye mota.
Yana ganina ya taso daga inda yake ya bud'e mini na shiga na zauna sai a lokacin na ji wasu gagariman hawaye masu radad'i sun k'wace mini. Wato ni kuma haka kaddarata take, ina ro'kon Allah Ya ba ni ikon cinyeta ya kuma saukakawa yaran nan rayuwa ya basu hakurin maraici.
Ina komawa gidan na samu Hauwa da Momi zaune a falo, amma babu cikakkiyar sakewa a tsakaninsu Hauwa ta yi zaman gadara da ki ce kule na ce miki cass domin kuwa fuskarta tamkar kunun tsamiyar da ya kwana a rufe. Kusan a tare suka amsa sallamata.
Kwarai da gaske na yi kokarin danne abinda nake ji a zuciyata game da al'amuran dake faruwa. Na nemi wuri na zauna babu yabo babu fallasa nake kallonta ina sake nazari akan al'amuranta. Ta tsuke sosai ta yi fayau abinka da mara jiki da gasken ne bata da lafiyar domin alamu sun nuna babu wani kuzari da karsashi a tare da ita.
Ita ta fara gaishe ni a tsanake na amsa ido na a kanta ina sauraran abinda take tafe dashi ta gyara zamanta kad'an tana kallona sai ta sauke ajiyar zuciya a hankali
Ta ce." Amina na shigo nan ne saboda ke domin mu tattauna abubuwan dake faruwa da yaranmu, Allah Ya ga zuciyata ban shigo cikin rayuwarku da wata niyya ta cutarwa ba, kuma ban had'a kai da Salim domin ya ci mutuncin Kamalu ba, asali ma abinda yake aikatawa ba ni da masaniya sai bayan ya aikata din nake samun labarin." Ta yi shiru tana sauke ajiyar zuciya a karo na biyu kafin ta cigaba da cewa."
Yana da kyau a matsayinki na uwa mai hankali ki yi nazari mai kyau Amina idan hankali ya 'bata fa nutsuwa da dattako ake sanyawa domin nemansa bai kamata ace kin d'auki munanan shawarwarin da ba za su zama silar gyar........Hauwa ta katse ta cikin fusata." tana fad'in "Ai dama ban ce kin shigo gidan nan domin ni ba Maryam, ko kuma kin ji na ce miki kin shigo ne da mummunar niyya. Kin tsargu ashe ai shi mara gaskiya dama kullum cikin zullumi Hajajju ki dube ni da kyau ki ga ni, a waye nake k'warai babu wata kinaya da za ki yi mini kafin ki san Amina da yaranta ni na santa na kuma zauna da ita. Idan har mijinki ya gaya miki cewa da hannuna wurin matakin da Kamalu ya d'auka bai yi miki k'arya ba, ga ni a zaune ai ina jiran hukunci tunda ku kun iya take gaskiya da gangan."
Cikin rashin sukuni na ce." Hauwa menene don Allah, duk cikinmu nan babu yaro karami tunda har ta shigo domin mu tattauna magana dan samun daidaito bai kamata wasu maganganu mara dad'i su biyo baya ba kuma."

Ta ja dogon tsaki tana fadin
"Kina jin irin jirwayen da take yi mini ai, ai mu 'yan iska ne marasa 'yancin kai tunda mijinta haka ya nuna mata ba mu da mutunci da kima sannan ba

mu da sirri komai muka yi a tambad'e ita nata sirri koyaushe cikin danda'be shi yake baya so kowa ya ji. Bazan jure d'aukar cin kashi daga 'bangaranta ba wallahi tallahi."
A nutse ta ce." Ba halina ba ne raina mutum Hauwa, kuma kamar yadda ki ke hasashe hakane maigidan ya gaya mini komai ke ce ki ke ko'karin ganin lallai sai an yi 'batacciya domin kuwa abinda muke ta bunnewa dalilin gudun rikici mai muni ke ki ka gayawa mahafiyar yaron nan, kuma ki ka cire nauyi da kunya ki ka dubi tsabar idon yaron nan Kamalu ki ka gaya masa to kin fad'a kin ji dadi kuma in sha Allahu abinda ki ke fata ba zai faru ba da izinin Allah."

Hauwa ta mike tsaye tana huci ta ce." Kin yarda yaronki mahassadi ne, kuma sharri ya yi wa Kamalu ko ba ki yarda ba,  ke yanzu don girman Allah ba ki ji kunya da nauyi ba
ai ita karya fure take bata 'ya'ya wallahi ni dai Hauwa Maryam ba ki isa ki siye ni da kudi da abin duniya ba. Wannan gingimeman sharri da d'anki ya alak'anta marayan Allah dashi saboda rashin adalci da son zuciyarku sai ku ja baki ku yi shiru babu wani mataki da ku ka d'auka.  Sannan kuce ba za a yi magana ba, to ni na sayi rikicin don girman Allah ki d'auki mataki a kaina. Kenan wannan ya nuna kun sake bawa yaron lasisin ci gaba da aikata abinda yake yi dalili kun nuna masa akan daidai yake, ke da mijinki kun daure masa gindi saboda kun tara abin duniya kuna ganin kun fi karfin hukuma ko? to  ku d'aukaka k'ara don Allah allura ce zata tono garma menene ba mu sa ni ba Maryam na fad'a din idan ta yi miki zafi ki kaini 'kara ko kisa tsinken tsire ki tsire ni!"

Na tashi tsaye da sauri
  na tare ta tare da mayar da ita kan kujera   na zaunar sai huci take yi tabbacin a fusace take kuma a shirye take da duk abinda zai faru.
Hayaniya ta fito da Baba Tabawa daga kicin tana fad'in." Mai yake faruwa ne don Allah ku yi aiki da hankali da girman shekarunku kada hayaniyarku ta d'auki hankalin yaranku k'ananu har su fahimci abinda yake faruwa, kun san dai yaro da ri'ke abu a zuciyarsa...

Littafin gudun aure na kudi ne, don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Cikin numfasawa Hauwa ta koma ta zauna tana huci! ita kuma Momi ta yi 'kasa da kanta k'walla cike a kwarmin idonta. Alamu sun nuna cewa ba ta iya fad'a na cacar baki ba koda fad'ansu ya yi tsayi da Hauwa ita za ta kaita kasa.
Har cikin zuciyata ban ji dad'in abinda ta yi mata ba duk da cewa duka su biyun ban san menene  a cikin zuciyoyinsu ba don haka ba daidai ba ne abinda ta yi tsinka na k'asa da kai ma tozarci ne ballantana wanda yake sama da kai ashekaru. Ni da ita duka haihuwa ce ta janyo mana domin kuwa da yara ba su had'a ba ina ganin babu wani dalili da zai sanya na yi sa'insa da ita akan namijin da ba shi da wani tabbas. Tun farko itama Hauwan da ta

d'auki shawarata abinda yake yi akan matarsa ba zai dameta ba tunda ta san tafi amfanarshi fiye da ita ko a wurin tarayya ta aure ne. Kuma ita ce uwar mai sunan mahaifinsa Ibrahim Khalil, uwa uba kuma 'yar uwarsa ta jini. Hauwa ba ta fi ni kishi ba wallahi kawai na fita ha'kuri da juriya ne dalilin gwagwarmayar da na yi a rayuwa ita ba ta yi irinta ba.
BabaTabawa ta koma kicin jikinta duk a sanyaye bayan cikin hikima irin ta manya ta yi mana nasiha aka ci sa'a kuma Hauwa bata k'alubalanceta ba.
Falon ya yi shiru bayan gushewar baba Tabawa daga wurin babu wanda ya sake magana. Ita Momi din tunda ta sunkuyar da kanta kasa ba ta sake d'agowa ba tabbatacin ta ji ciwon irin tijarar da Hauwa ta yi mata.
'Dagowar da za ta yi kuwa sai ya yi daidai da kwaranyowar ruwan hawaye a dakalin fuskarta. Ba ta yi yun'kurin gogewa ba sai ta kalleni ta fara magana cikin karaya da zullumi." Amina ni na haifi Salim amma wallahi ba na goyon bayansa akan irin abubuwan da yake aikatawa na rashin kyautatawa. sannan na sake jadadda miki babu yawuna ka haifi d'a ne kawai amma ba ka haifi halinsa b..... Hauwa ta yi saurin cewa." Kuka ai yanzu ki ka soma in sha Allahu rabbi Hajiya kina
fama da gagararan d'anki da ki ka kasa sarrafawa ina ke ina iya yi wa yaran wasu tarbiya wallahi ki ji tsoron Allah da Annabi, ga shi dai da bakin ki kin fad'a cewa Salim baya jin maganar ki, sannan nan Nusaiba ta shigo har gida ta yi mana rashin kunya, ina tarbiya anan kina so ki lalata mana yaranmu ne, ko kuma kina so su yi koyi da abinda yaranki suke yi duk a had'u a yi mutuwar kasko gabad'aya ko ba haka ba ne."
Shiru ta yi ba ta ce mata komai ba. Na dube Hauwa da ta kasa zaune a kan kujera sai zabura take yi kamar ta yi tsalle a gabanta ta rufe ta da duka.
Gyada kaina na yi ban ce komai ba na mayar da hankalina kanta domin sauraran abinda take cewa." Na nunawa Salim takaici da 'bacin raina na kuma gargade shi akan kada ya kuskura abu mafi muni ya sake faruwa irin haka. Ina kwance cikin ciwo jiya na samu labarin doki-in-doka da ya shiga tsakaninsu. Wannan shine abinda ya fi tayar mini da hankali na ce kina ina har hakan ta faru. Ban haifi Kamalu da Yusi ba, amma yau zan gaya miki wani abu da nake ji game da yaran nan a zuciyata wallahi ina sonsu fiye da yadda ki ke tsammani. Yadda nake jin yaranku gabad'aya a raina haka nake jin wanda na haifa. Ina rokonki da Allah da annabi kada ki yanke kyakykyawar ala'kar dake tsakaninmu. Kada ki yi yun'kurin datse k'akkarfan zumuncin da yake tsakanin Adamu da Yusuf domin kuwa d'azu Adam ya je mini cikin damuwa cewa kin tura yaran nan kano, ki yi hakuri yara su dawo mu cigaba da rayuwa cikin aminci na yi miki alkawari wani abu makamancin wannan ba zai sake faruwa ba. Kuma in sha Allahu Salim zai shigo ya baki ha'kuri komai ya shige da izinin Allah."

Ta gama maganar tana sanya hannu domin share hawayen da yake ta tsiyaya a fuskarta. A nutse na ce." Ki yi hakuri ki daina kuka akan wannan lamari Momi wallahi ban k'ullaceki ba, kuma ni har abada akan yara ba zan yi rigima dake ba, amma ina so ki sani ce wa muddin Kamalu da Salim na tare a Inuwa daya to sa'bani ba zai daina giftawa a tsakaninsu ba. Abinda ba na

fatan ya sake faruwa. Ba wai ba ki isa ba ne, kin fi karfin komai a wurina domin ban mance alherinki ba, ki yi hakuri yara dai har abada sun bar nan in sha Allahu suna can hannun dangin Babansu sai dai su zo da ziyara. kuma ban isa na yanke zumuci da ala'ka ba tunda ai ba ni na had'a ba......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki

Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*88*
Ta yi shiru tana gyad'a kanta kafin daga bisani ta yi wani murmushi da babu annashuwa ta ce." Shikkenan ba zan karya miki rantsuwarki ba Amina tunda har kin rantse amma ya za a yi da kayansu akwai takardun Yusi na makaranta shi ma Kamalu akwai wanda na sanya aka yi masa domin na gama shiri tsaf za su tafi jami'ar musulunci ta Madina makarantar da Salim ya kammala domin  samun horo fannin addini da al'kur'ani tare da hadisan Annabi Muhammadu S.a.w."
A nutse na ce." Babu damuwa duk abinda ya danganci nasu ne za ki iya aiko mini dashi sai nasa a mota a kai musu in sha Allahu rabbi, na gode sosai Allah Ya saka miki da alheri."
A sanyaye ta amsa da "Amin." Kafin ta yun'kura da kyar ta tashi tana gyara madaidaicin hijab din da yake wuyanta ta ce." Zan shiga gida, Allah Ya ba mu alheri."
Ni kadai na amsa mata. Hauwa kam uffan ba ta ce mana ba har muka 'kare maganarmu. Ta kama hanyar fita jikinta  a sanyaye.
Gabad'aya muka bi ta da kallo tana tafiya a hankali da rashi kuzari.
Sai bayan da ta fita ne Hauwa ta ja tsaki tana fad'in." Sai ta d'an ban tausayi wallahi."
Na dubeta a hankali na ce." Hauwa zan gaya miki gaskiya abinda ki ka yi wa matar nan ba daidai ba ne, don Allah ko don gaba kada ki sake kwatantawa ko so kike ki kàrasa gawar da ba ta ki ba. Kina kallon fa a yanayin da take ciki amma sai tsalle ki ke kina han'karo kamar za ki kai mata duka. Takaici abinda ki ka yi mata ne fa ya sanyata kuka. Ki duba shekaru da kuma d'awainiyar da take yi da yara don Allah."
Dan murmushi ta yi sai kuma ta ja tsaki a karon da babu adadi ta ce." Ta yi kukan jini ma, ni ina ruwana, sau nawa a sanadinta ana sanya ni kuka, munafukar banza kawai duk abinda take yi wallahi da niyya take yi ai sanin zuciyar mutum sai Allah."
Na gyad'a kai ina sake ce wa." Magana dai ta mutu Hauwa don Allah ni dai kada hakan ta sake faruwa kin ji."

Ta'be baki ta yi tare da furta." Haba ko yanzu na buga na bada ruwa wallahi zuciyata wasai nake jin ta. Murmushi takaici kawai na yi na yun'kura na tashi cikin zuciyata nake fad'in ba za ki ta'ba canzawa ba Hauwa, ba ki takali rigimar kina jin dad'i ba abinda zai biyo baya shine damuwar domin kuwa nasan akwai rikici akwance a tsakaninmu da shi uban gayyar. Shiga ta d'aki da kamar minti ashirin na fara jin hayaniya na tashi falo. Murya Hauwa a sama da wata murya da na kasa tantance ko ta wacece. Cike da zullumi da fargaba na fito falon na same su a tsaye cirko cirko har da yaranmu k'ananu a tsaye kusa da baba Tabawa dake ko'karin shiga tsakani.
Nabila ce 'kanwar Momi mutuniyata  ce sosai kuma tun lokacin rasuwar Alhaji Amadu muka kulla zumunci don har musayar lamba muka yi. Sai ta

d'an ja baya da ni ta rage kiran wayata bayan auran 'yar uwarta da maigidan. Ni kuma ban ta'ba nuna mata komai ba don wasu lukutan har magana nake yi mata idan na ga ta d'ora status a Whasap amma dai duk da hakan ta kasa sakin jikinta kamar lukutan baya.

Tana tsaye cikin shiga ta alfarma dama can 'yar gayu ce tunda itama tana taba kasuwancin irin na 'yar uwarta business take yi sosai zannuwan gado takalma da dogayen riguna har dashi take yi irin na manya maza da mata tunda ina gani a wasu lukutan tana dorawa a status dinta tana juya kudi itama yaranta biyu kacal duk maza tunda auranta ya mutu ta famtsa duniya itama har 'kasashen waje take zuwa sarin kaya..

"Ba ku isa ku kashe Momi da bakincinku ba Hauwa. Idan ba zata iya ba, ni zan kar'bi rigimar akan me? me ta yi muku da za ku tisa ta a gaba, masifar yau daban ta gobe daban tunda ta auri mijinku kuke yi mata bita da 'kulli kun had'e mata kai me ya yi zafi
mace tana sonku da zaman lafiya, tana d'awainiya da yaranku amma kuna cin dunduniyarta. Idan kun had'e mata kai sai me? Mijinta yana sonta fa, ai duk maccan da ta samu soyayyar namiji itace mowa kowa ya iya allonsa ya wanke
kuma ita alheri a jininta yake, wallahi ba za mu lamunta ba, za mu iya d'aukar kowane irin mataki akan abinda kuke yi."

Ido na zuba mata kawai kaina ya gama d'aurewa da maganganunta amma ba zan ce mata komai ba Hauwa kadai ta isheta tunda dama mai neman kuka ce.
Aikuwa ta bugi kirji har tana had'awa da tsalle tana fad'in." Karya banza da wofi an had'e mata kan don Allah ku d'auki mataki, matsafa masu kauce hanya domin neman duniya menene ba mu sani ba, dube ki don Allah sai kace tsohuwar karuwa tunda ki ka shigo falon nan ya game da 'karni da warin zunubi, kuna haura kan dutse fa ai ba abin mamaki ba ne don 'yar uwarki ta zama mowa a gidan nan, mun san komai mun ji labari
asalin dukiyar da uwar guzumar taku ta tara daga majiya mai tushe cewa kudin tsafi ne uwarku da ubanku ta bawa gumaka suka shanye jininsu. Sannan 'dan uwanku da aka tsinci gawarsa an kwakule masa Ido tare da cire masa 'ya'yan maraina haka aka ce da sanya hannunta. Tun a wancan lokacin kowa ya sheda matsafiya ce shine yanzu ta fake da gina gidan marayu taimakawa mabukata da sadaka domin yi wa Allah a dubara, in sha Allahu ba za ta yi karshe mai kyau ba
Har mu za a zo a yi wa wata burga, ko kuwa mun ce ta yi dawainiya da yaranmu ne? Ita taga zata iya. Mu dai in sha Allahu ba zamu rayu da kudin haram ba. Ba zamu fake da Allah da addini mu ciyar mu tufatar da kudin jinin mutane ba."
Nan da nan Nabila ta rikici sai ta fara rawar murya idanuwanta suka ciko da ruwan hawaye ta ce." Wallahi tallahi Hauwa sai mun yi shari'a dake sai kin

tsaya a gaban alkali kin bada sheda akan abinda ki ka fad'a akan 'yar uwarmu wallahi ba zamu bar wannan maganar ba
ba za mu yarda."

Ta ce." Ashe babu dadi k'azafi ko. Mai yasa kuka take gaskiya da gangan, yanzu ke Nabila har kina da bakin da za ki zo ki tsaya a gabanmu da wata banzar magana. Ki je ki tambayi 'yar uwar ki irin zaman da muke yi da ita a gidan. Ai ba a banza ta ri'ke mana yara ba. A shirye nake ki kalleni da kyau babu wata 'yar iska da ta isa na ji tsoronta wallahi."
Nabila ta kasa cewa komai domin ta yi mutukar k'aduwa da jin maganganun da suka fito daga bakin Hauwa. Duk yadda ta dinga kokarin hana kanta kuka hakan bai samu ba cikin gaggawa ta kama hanyar fita ba tare da ta iya mayar da martani ba.

Cike da mutuwar jiki na dubi Hauwa da take ta numfarfashi na ce." Tsakani da Allah Hauwa idan rai ya 'baci yana da kyau a sanya hankali da tunani. Yanzu ke don Allah a ina ki ka ji wannan maganar kada fa ki d'auri kanki Hauwa mai ya yi zafi ne, ni dai idan har a kaina ki ke wannan balo'kokon to don Allah ya isa haka, yaran da suka asassa wannan rikicin na d'auke su da gidan fakat mu zauna lafiya, babu ruwanki da matar nan da duk abinda zai shiga tsakaninta da mijinta a kan hakkinki kawai ya kamata ki yi magana, amma ki yi kokarin kawar da kanki daga barin ji da ganin abinda yake yi a kanta."
Baba Tabawa ta jijjiga kanta cikin alhini da damuwa ta furta." Don Allah ku zauna lafiya, wallahi ba na jin dad'in abubuwan nan da suke faruwa."
Tsaki ta ja kafin ta ce." A shirye nake da abinda zai biyo baya Amina, wallahi yadda na tsani mutuwata haka na tsani matar nan, munufuuka ce, mai son zuciya gabad'aya ta juyar mana da kan miji, ai kafin ya aureta muna zaune lafiya da sauki akan abinda yake yi yanzu, babu wadda yake gani da mutunci face ita. Ta dabaibayi shi ta ko'ina ta asirce shi sannan ta zo tana sadda kai kasa tana magana cikin alhini kamar wata mai gaskiya wallahi zuciyarta babu Allah
kuma abinda na fad'a ai ba k'aharu ba ne, ni ma ji na yi ana fad'a a duniya."
Daga haka sai ta tashi ta shige dakinta cike da neman tashin hankali.

Ni da Baba Tabawa muka bi ta da kallo cike da tsantsar mamaki. mai ya yi zafi haka, a ganina abinda take yi ai ni ya kamata na yi amma ban yi ba, ita lamarin nata yana nema ya wuce gona da iri fa, ba na so ta janyowa kanta gagarimin rikicin da zata yi nadama a gaba domin kuwa wad'annan maganganun sun yi tsauri kwarai da gaske kuma sun yi muni.

To ita rigima dama akwance take shiyasa tashinta bashi da amfani domin kuwa muddin ta tashi akan sha mutukar wahala wajan samun ruwan da zai kasheta. A wasu lukutan ma ana kashetan shaid'an da mukarrabansa suke shiga cikinta su yi kane-kane, su bugi wannan bangare su bugi wancan b'angare.

Lokacin da na ga kiran wayarsa hankalina ya tashi sosai dalili ban san mai yake 'kunshe a cikin kiran nasa ba, daga jiya zuwa yau abubuwa masu muni sun faru wanda na tabbatar da cewa muddin ba a kai zuciyoyi nesa ba to rayukan kowa zai 'baci har da wad'anda ma ba su ji ba, ba su ga ni ba.
Na daidaita yanayi kwarai da aniya ban bari raunina ya bayyana ba na d'aga wayar a nutse gaisheshi na fara yi bai amsa mini ba ya ce." Kai ni 'kara wurin Mahaifiyata bai gamsar da ku ba har sai kun had'a ba ki kun cutar da baiwar Allah ko Amina?"
Na ce." Ban fahimci maganarka ba."
"Nabila ta kira ni yanzu ta cikin tsananin damuwa tana fad'in irin abinda kuka yi mata yanzu daidai kenan Amina, ko kina so ki nuna mini hassadarki a fili domin Allah Ya suturta Maryam ta fi ku kyau da ilimi da gogewa ta fi ku dukiya da kyauta da tausayi, kana ta fi ku mutunci da karrama dan adam. Idan har za ku yi kishi akan soyayyar da nake yi mata wannan ba zai dame ni ba, tunda zuciyata ita ta za'ba a madadinku, amma ba zan lamunci cin zarafi da sharri ba, zan shige mata gaba domin ganin an hukuntaku bisa sharrin da ku ka yi mata mai mutukar muni da razanarwa......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma company yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*89*
A nutse na ce." To shikkenan muna sauraran sammanci a shirye muke ita Maryam tana da kai Tajo, Amina da Hauwa kuma suna da Allah da Annabinsa sai maganar da ka ke yi akan cewa muna yi mata hassada wallahi tallahi ni ban ga abin 'kyashi da b'akinciki a tare da wannan kwalmad'addiyar matar taka ba mai kama da mai cutar kanjamau ba, kudi da kake magana tana da su
kasan daidai gwargwado nima ina da su na halali babu wata mummunar hanyar da na bi wurin nemansu gumina ne, halak dina ne, babu wani mahaluki da ya ta'ba ba ni kwabonsa da zummar na yi jari, Ubangijina ya rufa mini asiri sannan
Ya taimake ni ban ta'ba ro'konka abin hannunka ba ina ga dana ta'ba neman wata alfarma a wurinka to da
cin zarafin da za ka yi mini sai ya fi haka. Ban ta'ba cewa Tajo tallafa mini ba. Eh tabbas talaka ne ubana amma ba mai mutuwar zuciya ba, kuma kai kanka ka san ba a tsiyace ka aure ni balle ka goranta mini. Allah Ya yi mini rufin asirin da babu wani mahalukin da ya isa ya firgita ni da dukiyarsa. Kai kanka baka da abinda za ka burge ni ga gigitani dashi ta fannin arziki balle matarka. Ko yanzu ka sake ni ba ni da kaico wallahi domin ina da madogara don naga kamar kana tunanin zan yi b'akincikin rabuwa da wannan daular da aka ajiye ni a cikinta. Idan kana da ja akan maganata to jarraba sakina kaga abinda zai faru.
Na yi shiru ina sauke ajiyar zuciya cike da tsananin bacin rai na cigaba da ce wa." Tunda ka zama dan aike jani talau ka gaya musu mun shirya da ni da Hauwa mu tafi kotun koli idan ba 'haka to mai ya kawo rami? Menene na damuwa don an ce mata matsafiya ashe da gaske matsafiyarce to ka gaya mata jinina dana yarana wallahi tallahi ya fi karfinta sannan wallahi ita dai ba takai maccen da zan yi wa hassada ba sai kuma abu na karshe wanda

nake so ka sani cewa ni Amina Tajo ba a gabana yake ba balle har raina ya sosu domin hankalinsa ya karkarta can wani gefe, ai ita soyayya guda d'aya ce tun ta 'kuruciya kuma tuntuni na bada ita a wani wuri har abada kuma wani namiji ba zai ta'ba samunta ba a wajena."
Tsaki ya ja cikin kame-kame ya ce." kuna abu sai ka ce jahilan farko. Duk da wanda ya ji wannan sakarcin da kuka yi ba zai yi muku kallon girma da mutuntawa ba."

Da sauri na ce." Ahaf to mu din mun gaya maka cewa muna so a yi mana kallon girma ne. Ai ba mu iya abu don duniya ta yaba mana ba. Riya ai babbar masifa ce da take saurin cinye dukiya da imani, Allah muke so ya yaba mana ba wasu jahilai b...
kashe wayarsa ya yi da sauri bai bari na kàrasa maganarta ba. Ban damu ba, ni ma na ajiye tawa wayar zuciyata kamar ta tsage saboda tsananin tashin hankali da mamaki!

To ni ina ruwana da har sunana ya fito a rigimarsu asalima lokacin da suka fara bana wurin mai yasa ita Nabila ta yi jimilla ta had'amu mu biyu. Shin da yawun ita Momin hakan ta faru ko kuwa. Wannan amsar ba ni da mai bai ni ita dole sai shi ko ita Nabilar da ta kira shi a waya ta sanar da shi abinda ya faru.
kafafuna suka dinga kyarma tsabar rud'u da al'ajabi wannan masifar fa ita na dinga gujewa saboda yanzu har ga Allah ba ni son abinda zai daga mini hankali domin zuciyata ta jima tana shakar damuwa da rikici da tashin hankali. Bayan haka kuma Ina tuna irin alkawarin da na yi wa Baban Saude ba ni so ya ga kamar na sa'ba maganarsa shiyasa nake ta ko'karin ganin na danne Hauwa domin kada lamarin ya yi tsamarin da zai kwa'be. Ni dai aka yi wa da yarana, na yanke hukuncin da nake ganin shine daidai da abinda ya dace a rayuwarmu shikkenan magana ta mutu idan zai lashi takashin matarsa ko a kwalar rigita shi ya ga zai iya.

Cike da mutuwar jiki na ja jikina a hankali na zauna gefan gado gabana na bugawa da karfin tun d'azu a lokacin da
Hauwa da Nabila suke musayar yawu nake jin marata na murda mini kad'an kad'an. Yanzu kuma sai abin ya kara tsananta gabad'aya ma saboda rashin nutsuwa da kwanciyar hankali na mance cewar akwai ciki na wata hudu da sati daya a jikina.

Na daddafa a hankali na shiga toilet na tsuguna da zummar fitsari jini ya biyo baya. Gabana ya yi tsananin buguwa wanda ya yi daidai da karuwar zubar jinin saman wandon da ke jikina.
Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! kalmar da na fara ambata kenan na tashi da kyar fafafuna na rawa na mayar da pant dina na fito tsakiyar d'akin na tsaya ina dawurwura alamun zubewar ciki ne ba wani abu ba.
Jikina na gyara cikin gaggawa na fito falo Hauwa tana d'aki sai Baba Tabawa a falon da yara sun zagayeta tana basu labari.

Kai tsaye d'akin na bi Hauwa tana kwance saman gado da wayarta a hannunta har yanzu babu sukuni a tare da ita ta tashi zaune tana kallona kafin ta ce." Ina kuma za ki je na gan ki da hijabi."

Wannan littafin na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na ce." Hauwa babu lafiya 'bari zan yi wallahi yanzu haka maganar nan da nake yi miki jini ne yake zuba asibiti zan je. Ta yun'kura ta tashi da gaggawa tana fad'in." Bari na sa hijab muje Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Da sauri na fita daga d'akin jin yadda  wani abu mai nauyi ya fado cikin pant dina. D'akina ana shiga da gaggawa na zarce toilet na yi sauri na tsuguna abun ya fado kafin wani mashahurin jini ya biyo baya da tsananin ciwon k'wankwaso da gwiwa. Bangon bandakin na dafe tare da rintse idona da k'arfi na kira sunan Allah ina jin shigowar Hauwa d'akin da yake ban rufe kofar toilet din sosai ba kawai sai ta shigo ta kamani itama sunan Allah kawai take kira tana fad'in." Shikkenan gashinan ma ya fita cikin sau'ki sannu bari yanzu na tura Masa'udu ya je pharmacy ya sayo miki wasu magunguña ba sai mun je asibiti ba in sha Allahu, Allah Ya takaita miki wahala duk abinda ya yi saura zai fito cikin salama idan an yi amfani da maganin."

Ban damu  da jin abinda ta ce ba tunda na san aikinta ne. Ni kaina dama ba ni son zuwa asibitin dalili ban shirya ya ji yanzu ba.

Ita da Baba Tabawa suka gyara toilet din tsaf. Baba Tabawa dai sai jajantawa take yi har da 'yar k'wallarta tana fad'in." Namiji ne gashinan har Ubangiji ya fara yi masa hallita.  Hauwa da suke aikin tare uffan ba ta ce mata ba ta yi mata shiru kawai. Ina zaune a gefan gadon Baban ta zo ta fita da wata leda a hannunta tana fad'in. "In banda abinki Hauwa ya za a yi a jefa d'an mutum a masai  ina gaya miki gashinan Ubangiji ya fara fitar masa da hallitarsa.
Ido na bi ta da shi Hauwa ta fito daga toilet din tana fad'in." Magana ai ta mutu Baba ki je ki kai a bunne shi tunda haka aka koya miki a makarantar islamiyarku ta mutanan da."
Na dube ta a tsanake na ce." Abinda ya fita za a binne?"
Ta gyada kanta tana fad'in." Haka ta ce, shine ta tattare ta zuba a leda wai ita dai ba da hannunta za a zuba d'an mutum a masai ba."
Murmushi kawai na yi na ce." Hauwa kin san mutanan da camfi, wasu fa har yanzu suna wanke mahaifa tsaf su shiryata da likkafani su bunne. Ko musulunci an ce bata da wani amfani
Ta ja tsaki tare da furta." Mu a asibiti ma wallahi tattarasu muke yi a buhu a kai bola. Bata da wani amfani face zaman da ta yi da d'anka a ciki."

Shiru ya biyo bayan maganarta kafin ta numfasa a hankali ta ce." Wallahi Amina sai na ji ina ma ace ni ce na samu wannan matsalar kin san Allah ba na k'aunar cikin nan da yake jikina zan iya zubar da shi ni ma."

Da sauri na kalleta tare da furta." Ni ai ba da gangan na zubar ba Hauwa tsautsayi ne tare da tashin hankali da kuma rashin nutsuwa ya zubar da shi, yanzu lamarinki  yana ba ni mamaki da tsoro wai shin me ya yi zafi ne don Allah don Annabi."

Ta yi shiru tana kallona da wani irin yanayi na damuwa. Na gyada kaina ina zullumi da tunanin yadda zan sanar da mai cikin ya zube ya amince kai tsaye ba tare da ya juya lamarin ba shine kawai abinda ya fi damuna a yanzu domin zai iya kulla mini sharri a wurin magabatana tunda dama yana jin haushina.
Ita kuwa na fahimci yanzu gabad'aya ta daina tsoronsa balle ta daga masa kafa

Sai da na ci abinci tukkuna ta gwada mini duk yadda zan sha magunguñan da ta bayar a rubutuce aka sayo mini sannan na kwanta ita kuma ta tashi ta fita. Bacci ne mai nauyin gaske ya d'auke ni wanda cikinsa na kasance cikin hargitsin mafarkai marasa ma'ana.
Shigowar kira a wayata dake gefena shi ya tashe ni cikin firgici na tashi zaune wanda ya yi daidai da tsinkewar jini da k'arfinsa wanda nake da tabbacin ya huda zanin jikina kuma babu makawa sai ya shafi mashinfidin da yake kan gadona.
Wayar na d'auka na duba Hamusu ne da sauri nasa a kunnena. Jin shi cikin nutsuwa ya sanya hankali ya dan kwanta kad'an na amshi gaisuwar da yake miki  kafin na tambaye shi su Kamalu da fara'a mai yawa a tare da shi ya ce mini gamu a ciki tasha a tare dama kiran da na yi miki kenan yanzu za mu wuce gida."
Na sauke ajiyar zuciya tare da furta." Alhamdulillahi, ka gaishe mini da Gwaggo idan an jima da daddare na d'an samu nutsuwa a lokacin zan kira ka sai mu kàrasa tattauna yadda za a yi."
Ya ce." To shikkenan anti   sai na jiki in sha Allahu."
Kashe wayar na yi na ajiye saman bedlamp kafin na zuro kafafuna kasa a hankali. Baba Tabawa ta turo d'akin  ta shigo. Sai na sauke ajiyar zuciya domin na ji dadin shigowartata.
Ta nufo ni tana fad'in." Sannu ai na shigo ya kai sau biyar ba ki tashi ba ga la'asar ta yi babu kyau bacci a irin wannan lokacin......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal

*90*
Na ce." Tunda na sha magunguñan jikina ya mutu amma dai ciwon marar da sauki alhmdullhi sai jinin da yake zuba shine abinda ya d'an ba ni tsoro.
Ta ce." Ai wannan dole ne sai a hankali zai dinga janyewa." Ban ce komai ba na tashi a hankali na nufi bandaki ina fad'in." Baba ki dan fito mini da wasu kayan tare da audiga sai ki miko mini."
Ta amsa cikin kulawa. Wanka na yi da ruwan d'umi na gasa jikina sosai na shirya a toilet din na fito. Lokacin har ta cire zanin gadon da ya baci ta shimfida mini wani tare da sanya turaran wuta. Ina fitowa ta shiga bandakin da bedsheet din a hannunta.

Bata fito ba sai da ta wanke zanin gadon tare da kayan da na cire ta fito dasu a boket ta fita can haraba domin shanyawa.
Sai bayan sallar magriba Hauwa ta sake shigowa ta duba ni, tana tambayata idan da matsala na gaya mata na ce mata babu komai na ji dadin magunguñan dana sha
Mun kai kimanin minti talatin a tare muna tattaunawa kafin ta fita.
A lokacin na samu sararin kiran Hamusu a waya gaishe ni ya sake yi kafin cikin inda-inda ya ce "Dama yanzu nake cewa bari na kira ki a waya gani nan tare da Gwaggo ma."
Na ce." Allah sarki ba ni ita to mu gaisa."
Tana kar'bar wayar cikin kulawa na gaisheta tare da tambayar yanayin jikinta ta amsa itama da kulawa.
Sai da na d'an nisa  tukkuna na fara yi mata bayanin duk abinda yake faruwa. Bata katse ni ba har sai da na kammala maganata kafin daga bisani ta ce." Hamusu duk ya yi mini bayani Amina kuma ai maigidan naki ma bai jima da tafiya ba mun jima muna tattauna magana akan lamarin rayuwar nan hakuri ake yi da d'a da dukiya duka babu wanda ya san mai amfanarsu sai Allah, kema ban ga lefinki ba don kin yanke wannan hukuncin ba ki yi lefi ba kin nuna jarumta kwarai da gaske."
Na sauke ajiyar zuciya a  hankali na ce." Shine dalilin da ya sanya na ce su dawo nan wurinku su zauna mu fadada harkokinmu na yau da gobe sai had'a hannu da Kawun nasu Hamusu wurin ganin sun kawo mana cigaba gabad'aya."
Ta ce." Kwarai hakan yana da kyau sai dai ni abu daya da ki ka yi anan shine yadda ki ka yanke hukunci ba tare da sanin mijinki ba, Amina ba ki yi daidai ba anan ai ya gaya mini cewar shi ma da kin sanar dashi ga hukuncin da ki ka yanke ba zai hana ki ba tunda da nan da can wurin naku duk daya ne. Sannan kuma Amina ina kara tausar zuciyarki da kyautata ha'kuri  a rayuwa saboda duk mutumin da ya nuna k'aunar abinka ya gama maka komai mu babu abinda za mu cewa bawan Allah nan domin kuwa ya rike mana ke tsakani da Allah kuma ya kula da abinda ki ka je masa da shi ya rike kamar shi ya haife shi. ki yi hakuri kin ji ko, daga yau kada ki 'kara yin hukunci ba tare da kin shawarci mijinki ba sai ya ga kamar kin nuna masa iyakarsa ne.

Jiki a sanyaye na ce." To Gwaggo ina jin dai Hamusu bai yi miki bayanin abinda ya faru ko?"
Ta ce." Ya gaya mini mana shi ma mijin naki da ya zo ya sake yi mini bayanin duk abinda yake faruwa tsakanin yaran."

Kaina ya yi masifar daurewa jin abinda take ce wa, gabad'aya tunanina sai ya tsaya cak! ya aka yi ya san abinda na shirya ko dai Hamusu ne ya munafurce ni  ya gaya masa. Ita kuma Gwaggo mai take nufi da wannan maganar wato ita ba ta kishin nata kenan, tun asali ban santa da son abin duniya ba balle na ce ya rud'e ta da kudinsa.
Na ji maganar Hamusu yana cewa anti abinda ya faru shine d'azu bayan na dauko yaran nan a tasha sai  na zarce dasu kasuwa domin saya musu kaya

da abubuwan buk'ata kamar yadda ki ka bada umarni. A hanyarmu ta dawowa wallahi Sukairaju ya d'auko Yallabai a mota zuwa airport ya hange mu don shi bai ma gan mu ba shi Sukairajun ne ya gaya masa shine fa ya sanya shi ya biyo bayanmu har gidan Gwaggo. Babu yadda zan yi anti dole ta sanya na gaya masa komai a gabansa Gwaggwo ta yi fad'a sosai domin kin san ni da ke ba mu gaya mata matakin da muka dauka ba, anan ta sake tabbatar masa da cewa ita ta bashi yaran tun lokacin kwanciyarta a asibiti kuma kyautar tana nan ba ta janye ba.
Wannan dalilin ya sanya shi d'aukarsu amma ya ce zai a jiye su a gidan Hajja tunda ba kya son zamansu a abujan. kyauta kuma ya kar'ba har abada."
Wani irin takaici marasa misaltuwa ya lullubeni. Mutumin nan ya zame mini bala'i ta kowace siga dole sai ya tan'kwarani. Ban san lokacin da wasu lafiyayyun hawaye masu zafi suka fara silalowa kumatuna ba. Kashe wayar kawai na yi na ajiye ina jan hanci zuciyata kamar ta buga. Lallai Gwaggwo ta iya yankan k'auna da nuna iko da gadara. Wai me yasa mutanan da suke hofintar da na su ne koda kuwa sun tabbatar da gaskiyarsu. Gwaggo bata san halin mutumin nan ba shiyasa take yabonsa har take yi masa kyautar d'an mutum. Tunda mutumin ya kutso rayuwata yake ko'karin raba ni da nutsuwa da farincikina. Ba na samun wata d'aya a cikin annashuwa ba tare da wata matsala ba. Yarana ni na haife su amma 'kiri-'kiri yanzu ba ni da iko da su, ban san inda aka yi haka ba. Hannu nasa na goge hawayen dake sauka a kumatuna sasaauci guda daya da na ji a zuciyata yaran na can hannun Hajja nasan suna hannu nagari ba za su wulakanta ba. Amma idan son raina ne gabad'aya yarana su bar shiga alfarma kowa su ci da guminsu su tufatar da kansu ta guminsu su kuma mori lafiya da kuruciyarsu. Ba ni da damar wata magana domin ba zan iya nuna rashin amincewata da abinda Gwaggwon ta zartar ba domin tunda yaran suke hannuna bata ta'ba nuna mini wani iko mai tsauri a kansu ba. Lallai mutumin nan ya dahu da sharri da ladabin 'yan shaye-shaye. Allah Ya saka mini.

Don Allah kada ki karanta littafin nan ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Can kamar saukar tsawa! na ji sautin muryarsa a falo. Gabana ya fadi sosai domin kuwa wannan sautin ba na sa ba ne aro shi ya yi. Asali muryarsa sanyi ne da ita ko fad'a yake yi asalin muryarsa ba zata gigitaka ba sai dai zafin ba'kaken maganganunsa.
Ban yi yun'kurin fita falon fa saboda bala'in haushinsa da nake ji a raina nasan dai dole zai shigo d'akin ya same ni. Baba Tabawa ta a shigo a gaggauce tana fad'in." Idan za ki iya fitowa falon ki fito Amina, mijinku ya shigo yanzu amma abin babu dad'i tsakaninsa da Hauwa."
Na ce." Ka kyale shi kawa Baba, fitowata ba zata amfanar da komai b.... Ban kai ga rufe bakina ba na ji kukanta cikin reshi tana fad'in." Ka kashe ni kawai Allah Ya isa tsakanina da kai."

Baba Tabawa ta ce. A gabana ya kai mata mari kusan uku a fuska.

Na diro daga gadon da gaggawa "Mari" Na furta da mamaki mai yawa, ai ba halinsa ba ne. Bar shi da ba'kar gaba da bakaken maganganu amma baya dukan mace. Bai ta'ba kai hannunsa jikina ba.
Daidai lokacin da ya ke ce wa." Ke kadai ki ka zo, kuma ke kadai za ki fi ce mini daga gida. Yara kuma ita na yi niyyar bawa Maryam zan bawa, ban yarda na bar muku su anan ba."

Tana kuka ta ce." Ai gadon rashin tarbiya muka yi da ni da kai. Tunda abinda ya yi Hauwa shi ya yi Tajo. Hajja ta saki nono ta bawa Uwani ni dai duka babu na za'ba, Allah Ya saka mini."
Ya sake kai mata mari ta goce tana fadin." Ni ma rabon shan wahala ne ya sanya ni auranka, kuma in sha Allahu mun rabu kenan har abada, kuma ka sani cewa wannan masifar daka 'kunsa mini sai ta bi rariya."

Tsakaninsu na shiga duk kuwa da rashin kuzarin da nake ciki ina fad'in." Menene haka don Allah, kada fa zuciya ta d'ebe ka ka zo kana nadama, me ta yi maka kake dukanta."
Ya ce." Matsa gefe Malam ina ruwanki wa ma yace ki fito?"
Na ce." To shikkenan had'a mu gabad'aya ka doka sai ka huce takaicinka, ai ba da hannu za ka yi dukan ba kasa wayar redio kawai."

Baba Tabawa ta dinga fad'in." Don Allah Yallabai a yi hakuri babu girma a wannan lamarin kada yaran nan su ankara su fito, ka yi hakuri a matsayinka na babba kuma jagora."

Cike da b'acin rai ya furta." Baba wad'annan matan ba su da mutunci wallahi sun hana ni nutsuwa mussaman 'yar iskar yarinyar can Hauwa ta rikita mini gida menene amfanin zamana da ita tunda ba ta son zaman lafiya."

Na ce." Ita kuwa take da amfani wallahi ka je ka 'kara tunani idan kana cikin hayyacinka Hauwa ba abar wulakantawa ba ce."
Ya yi shiru yana muzurai kafi ya dubi Baba Tabawa tare da ce wa." Ki had'o mini kan yaran nan ki biyo bayana da su. Da sauri cikin bin umarni ta ce." In sha Allahu ranka ya dad'e.
Ya juya ya fita da saurin gaske.
Na dubi Hauwa da mataccen jiki sai kuka take yi gabad'aya ta fice daga hayyacinta. Kafadarta na dafa ina fad'in." Me ya faru?"
Tana goge fuska ta ce." saki na fa ya yi kuma na saku har abada wallahi."

Ta wuce dakinta da sauri. Cikin sagewar gwiwa na bi bayanta ta shiga bandaki sai na zauna gefan gado har ta fito wanka ta yi ta fara shiryawa tana yi tana kuka. Na ce babu fa inda za ki je wallahi ai saki daya ne ki zauna ku daidaita."
Shiru ta yi mini ba ta ce komai ba kuma ba ta fasa shirya kayanta cikin akwati ba.

Na yi jigum da mataccen jiki, wato dai mutumin nan in dai akan sha'ani na Momi ne baya ji baya gani, ai ban ta'ba tsammanin zai iya sakin Hauwa ba, a iya tunanina je ki gida ki huta kawai zai yi mata tunda itama zahiri ta yi abubuwa da yawa da za su tunzura shi idan kuma har an yi duba da matsananciyar dangantakar da take tsakaninsu tafi karfin wannan tozarcin duk kuwa da abinda za ta yi masa karfin zumunci da albarkar zuri'ar da ta ratsa tsakaninsu ba ta cancanci hukuncin saki daga wajensa.
Ina zaune zukud'un ina tunani lallai kamar maganar Hauwa da 'kamshin gaskiya ko dai matar nan ba a haka ta bar mutumin nan ba, kansa a juye yake wallahi domin gaba da gaban da muke yi dashi yanzu na karance tsaf ba a nutsuwarsa yake ba
yakan rufe ido ya yi cin mutunci ga kowa muddin aka ta'ba ta ko wani abu da ya dangance ta......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram.Normal what'sapp Gruop kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya

Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma company yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*91*
Don kyautawa tabbas Hauwa bata kyauta ba ni ma tun a wurin na nuna mata rashin goyan baya, kuskure ne mai k'arfi k'azafi ko tabbatar da abinda ba ka da shaida akai. Iyayen baiwar Allah nan daga ni har ita ba mu da masaniyar abinda ya kashe su. Mijinmu ta aura kawai bayan haka duka ba mu da wata ala'ka da juna. Wata'kila ita Hauwa ta jima tana bin 'kwakkwafi akan Momi din idan ba haka ba ta ina take samun irin wad'annan labaran masu muni. Tabbas idan gaskiya ne to Momi abar gudu da k'yama ce, idan kuma kishi ne ya rufe idon Hauwa ta k'irkiro maganar ta fad'a bata kyauta ba ta aikata abinda ba shikkenan ba, amma a ganina a matsayinsa na namiji jagora mai nisan tunani bai kamata ya zartar da wannan d'anyan hukuncin ba.
Gabana ya buga da karfin gaske a lokacin da na tuna irin abinda yake kwance ciki ya zube na nasa yara a mota ba tare da yawunsa ba. Idan ya sake ni akan hakan ba zan wani damu ba, ai na yi abinda na yi daidai gwargwado sai na ha'kura da auran ma gabad'aya idan na mutu na riski Yaya Aminu a matsayin matarsa ta aljanna tunda ban tafi da zargen igiyar auran wani ba.
Sai dai tsorona da fargabata shine ina shakkun ya sanar da Baban Saude domin kuwa yanzu shine yake tsaye akan al'amarina tun bayan sasancin da ya yi mana a shekarun da suka gabata. Kuma ba tun yau ba na lura da k'akkarfan zumunci da abotar da ta 'kullu a tsakaninsu. 'Bacin ran Baban Saude da tijararsa ita kadai nake gudu amma don ta kalubalen wannan mutumin baya damuna.
Jan kofar da Hauwa ta yi shine ya dawo da ni hayyacina na daga kaina da sauri na ga gilmawar fitarta da akwati madaidaiciya. Da azama na tashi na bi bayanta Allah Ya sa falon babu kowa tunda ya kwashe yaransa Baba Tabawa kuma tana dakinta. Na ri'ke akwatin ina fad'in." baki da hankali Hauwa ina za ki je a wannan daran ki yi tunani fa a abuja ki ke."
Ta ce." Sai me idan a Abuja nake zan iya kwana a tasha a halin yanzu domin na yi rantsuwa ba zan kara kwana a wannan gidan ba Amina."
Na ce." Ke ma fad'a kawai ki ke yi, an ji ya sake ki, amma ai gidan d'an uwanki ne kuma uban yaranki, sannan addini cewa ya yi idan an saki mace

ta zauna a dakinta ta yi idda idan da sauran rabo mijin zai iya mayar da ita kafin kammaluwar iddar don haka babu inda za ki je."
Shiru ta yi tana kallona can kuma sai ga hawaye shaa! murya a sarke ta furta." Wai saki Amina, ni mutumin nan zai furtawa saki ai ina ganin ko zai saki kowa wallahi ni ban cancanci hakan ba.
Murmushi na yi Ina nazarin maganarta, ashe shiyasa ta mike kafa take iyashege saboda tasan ta taka tudu biyu a iya wautarta duk iyashegen da za ta yi masa ba zai iya sakinta ko wani hukunci mai tsauri ba. Rauni da gajeran tunani shine abinda yake cutarmu mu mata amma duk inda muke tunanin akan sha'ani na maza wallahi sun shallake nazarinmu, mussaman na mu mijin da ya kasance makiri. Gabad'ayansu Allah
ya hallicesu ne daban da hallitar mata. Kuma dai dole duk isa da kasaitar mace sai dai idan ba ta yi auran ba.
Ta nemi wuri ta zauna tana share hawaye na zauna gefanta a sanyaye na ce." Ke ma fa kina da laifi Hauwa tunda naga irin abubuwan da ki ke yi nasan lallai akwai abinda zai faru wanda gabad'aya ba zai yi mana dadi ba. Na sha gaya miki ki fita daga sabgarsa da matarsa idan ma tsuguna mata zai dinga yi babu ruwanki da su amma kin 'ki ji, kin ga a cikin igiyoyin auranki uku daya ta girgiza ita nata suna nan daram!
Sai ta rufe fuskarta da tafin hannunta tana kuka cikin jajantawa kanta ta ce." Sai na gayawa mahaifiyarsa wallahi."
Da sauri na ce." Aikuwa da kin da'bawa kanki wuka Hauwa, kin san ya tsani fa a kai shi k'ara wannan yana masifar 'kona masa rai,kuma yana daya daga cikin abinda ya tunzura masa zuciya tunda ai dawowarsa kenan ya zo ya huce fushinsa a kanki nasan
kuma dole Hajja ta bi ba'asin komai idan har za a yi adalci a lamarin dole ke ma a nuna miki rashin gaskiyarki. Kuma da yawa mutane za su ce kin shigar mini fad'a ne mun taru mun had'e mata kai muna azabtar da ita fassarar da za a yi mana kenan. Ba za a taba duba kisan mummuken da take yi mana ba ta 'karkashinsa tunda sigar da ta biyo wurin wargaza mana zaman lafiya da nutsuwa mai wahalar fahimta ce ba kowane zai gane abinda yake can kasan zuciyarta ba sai Allah."

Ta bude fuskarta tana kallona ta ce." To yanzu ya ki ke ganin zan yi, ni dai wallahi gabad'aya hankali yana gida na gama shirya tafiya Bauchi."
Na ce." Ki yi zamanki ki kyale shi kuma don Allah kada ki sanar da inna Uwani kada sanadiyar hakan zumuncinsu ya raunana kin san mas'ala ta auran zumunci tana da wuyar sha'ani.
A sanyaye ta ce." Shikkenan ba zan gaya mata ba amma wallahi matar nan yadda ta sanya ya sake ni saboda ita sai na wulakantata."
Da mamaki mai yawa na ce." Wane irin wulakanci kuma Hauwa, ai kin gama wulakantata domin duk wasu maganganu masu muni kin jingina mata sai me ya yi saura. Ni fa wallahi masifar nan ta ishe ni haka
don Allah ki samu nutsuwa gabad'ayanmu fa babu yaro, yanzu ke za ki gyara auranki da zumuncin da yake tsakaninki da shi, na gaya miki idan kina so ki

samu nutsuwar zuciya don girman Allah ki fita sha'aninsa da matarsa, da sannu idan muna da hakki za mu gan su a rana."
Shiru ta yi ba ta sake cewa komai ba, ta dai sunkuyar da kanta kasa tana tauna lebanta tabbacin abin da ya yi mata ya yi mata ciwo a zuciyarta.
Sai wajejan tara da wani abu tukkuna muka rabu ta shiga d'akinta da zummar shan maganin ciwon kai ta kwanta dalilin kukan da ta ti'ka, abinci ma ni na bi bayanta da shi kafin na fito falo na zauna na ci nawa muna hira jefi jefi da Baba Tabawa wajan goma da rabi ya shigo Baba Tabawa da saurin gaske ta yi masa barka da shigowa ya amsa babu wata kyakyawar kulawar da yake yi mata domin mutuniyarsa ce sosai a wasu lukutan har barkwanci suke yi ita dashi amma abin mamaki ko yau ni ma ban ji dadin abinda ya yi mata ba.
Ta dube ni tana fad'in." Ni ma kuna nema ku shafa mini kashin kaji Amina, Yallabai kamar fa haushina yake ji duk yadda nake ko'karin ganin na gyara ku abin zai shafe ni.
Yadda ta yi maganar da alhini da damuwa sai ta ba ni tausayi da dariya na d'an yi kad'an kafin na daidaita kaina na ce." To ke ina ruwanki Baba, kawai dai ransa ne a b'ace shiyasa ki ka ga bai amshi gaisuwarki da kulawa ba, kada ki wani damu ai ba ki da lefi."
Ta yi shiru tana jijjiga kai har da tallafe ha'ba. Na yi dariya sosai ina fad'in " Hajiya Baba Tabawa ta mu ta gargajiya."
Ta dube ni da yanayi na zullumi amma ba ta ce komai ba. Daga can barandar samansa na ji maganarsa na juya da sauri yana tsaye hannunsa zube a cikin jallabiyar dake jikinsa ya ce." Zo."
Na yun'kura na tashi da tahamidi da kuma addu'ar rinjiye wannan lokacin nake jira, na kuma ji dad'i da ba a ja dogon lokaci ba gwara a yi ta ta 'kare kawai.

Na d'auka idan na shiga d'akin zan gan shi a rikice cikin matsananciyar damuwa, abinda ya ba ni mamaki bai wuce ganinshi a zaune a gefen gado da waya a kunnansa yana magana cikin rarrashi da wata kalar murya wadda tun tsayin zamana da shi ban san shi da ita ba.
Jikina ya d'an shika kad'an amma lokaci d'aya ban bari ya fahimci raunina ba, na zauna gefansa hankali da jina yana kansa domin fahimtar da wa yake waya.
Kasa gane kowacece na yi domin da da farko na d'auka Momi ce sai da na ji yana kiran Maman Hanif tukkuna na yi tsai ina tunanin wacece wannan kuma. Tunani na ya katse lokacin da na ji sautin maganarta cikin reshin kuka ban dai ji mai take gaya masa ba, amma gabad'aya yanayin yadda take magana shi ya tabbatar mini da cewa cikin tsananin b'acin rai take. Na dinga nanata sunan a cikin raina Maman Hanif domin na kasa gane wacece can nazarina ya hasaso mini Nabila kanwar Momi ce tabbas ita ce babban yaronta sunansa Hanif hakane yakan zo wurinsu Adam a duk lokacin da aka yi hutun makaranta.
Ajiyar zuciya na sauke na sake kai duba na gare shi ya tak'arkare yana ta rarrashi da ban ha'kuri na gyada kaina ina jimanta matsayin momi da

alhalinta a zuciyarsa. Maganar abinda ya faru tsakaninta da Hauwa suke tattaunawa da 'kyar dai da jibin goshi da irin rausayar da kai da muryar da yake yi ya rarrasheta ta ha'kura tare da kudirin janye 'karar da suke ko'karin shigarwa akan Hauwa. Na ji dad'i dai da bai gaya mata irin hukuncin da ya yanke ba ba domin a yadda yake a zaburen nan abu ne mai sau'ki ya gaya mata cewa ai ya saki hauwa ba. Wasu lukutan kuma zurfin cikinsa yakan burge ni ya kuma yi masa amfani. Tabbas Hauwa bata kyauta ba, kuma ni ban ga laifinsu ba don sun ce za su kai ta 'kara matsalar kawai idan har aka bari hakan ta faru gabad'aya rayukan kowa ne zai b'aci shiyasa Annabi ya yi hani da tayar da masifa domin idan ta tashi kafin ta kwanta sai an d'auki wani lokaci.
Ya kashe wayar ya dube ni fuskarsa kadaran kadahan. Kafin ya yi gyaran murya ya ce." Ina alkawarin da muka yi ni dake ranar da baban Saude ya yi mana sulhu....
Kafin na ce wani abu kira ya shigo wayata dake saman cinyata.
Hajja ce sai na d'auka a tsanake muka gaisa da kulawa kamar koyaushe ta ce." Ai ya zo mun jima da shi kuma ya gaya mini dukkanin abinda yake faruwa dalilin da ya sanya na ce ba zan bari har sai gari ya waye ban yi magana dake ba. Da farko dai ina mai kara baki ha'kuri ina kuma kara yaba miki bisa ko'karin ganin kin yi hakuri da duk umarnin dana ba ki. Babu shakka kin nuna mini cewa ke din 'yar halak ce na gode sosai Allah Ya yi miki albarka Amina sai dai a wannan lokacin ba zan tauye miki hakki a matsayinki na uwa mahaifiya ba. Ko daya ban ga lefinki ba domin tsira da mutunci ai yafi tsira da kudi babu wani dalilin da zai sanya yara su zauna a wurin da babu daraja kuma babu mutunci. Hajiya Maryam tun kafin Tajo ya aureta shedar da muka yi mata mutuniyar kirki ce kuma har yanzu akan hakan muke kallonta. Amma tabbas tarbiyar yaranta akwai nakasu ba wai na za'bi Kamalu na fifita shi akan Salim ba. Kafin na kira ki a yanzu na zauna da Kamalu cikin hikima na tambaye shi ya kuma yi mini bayani tsakaninsa da Allah wanda nake da tabbacin haka siddin ba zai kirkiri karya domin ya 'bata Salim ba." Ta d'an yi shiru tana sauke numfashi kafin ta cigaba da cewa." Sannan mijinku na nuna masa kuskuransa sosai duk da ya kawo mini hujjarsa amma ni bata gamshe ni ba saboda banga dalilin da zai sanya ya ce a rufe miki abinda ya shafe ki ba. Kenan babu adalci a ciki koda ya yi hakan ne domin yin nazari akan lamarin kafin ya yanke hukunci ta 'bangaranki ba za ki ta'ba gamsuwa da cewa bai hofintar da  naki ba, ma'ana ya karkarta a bangare daya da tabbacin nan ne da gaskiya. Abu ya faru wanda ya sosa ran kowa ina kuma sake baki ha'kuri domin a ko'ina ina irin wannan matsaltsalun suna faruwa. Kin yi daidai da ki ka turo yara nan ni kin burge ni kwarai kuma kin yi hankali da ba ki tunkari Maryam da tashin hankali ba. Ina so ki gaya mini abinda yake ranki don Allah kada ki ji kunyanta da kuma nauyi yaran nan kin amince da zamansu a hannuna kamar yadda mijinku ya ba ni su amana ko kuma na sanya Magaji direba gobe ya mayar da su gidan Gwaggwon gobe, idan har hankalinki zai fi kwanciya da hakan don Allah ki gaya mini gaskiyar abinda yake cikin ranki."

Sosai jikina ya yi la'asar na gaza cewa komai saboda tsabar nauyi da nazarin ya zan yi na ce mata ba ni son zamansu a hannunta wanda nasan ba wurin da za su cutu ba ne.
Maganarta ta dawo da ni hankalina. Na ce." Hajja ni dama zamansu ne kawai ba na so anan din tunda har suna nan wurinki babu komai wallahi ai dake da Gwaggon duk daya kuke a wurina na amince su zauna Hajja Allah Ya taya ki riko."
Cike da farinciki ta furta." Aikuwa na gode sosai da wannan alfarma dana samu, ni ma zan samu ladan rik'on maraya ashe na gode Amina, in sha Allahu kuma yaranki ba za su yi kukan maraici ba, Allah Ya yi miki albarka kin jima kina yi mini alfarma ni kuwa da me zan saka miki "
Tak'arasa maganar da rawar murya. Sai hankalina ya tashi jin tana shirin fashewa da kuka na ce." Haba Hajja ni din taki ce fa balle kuma yara don Allah ki daina yi mini godiya babu ita a tsakaninmu, addu'ar da ki ke yi mini da ita kika saka mini ita kadai ma ta ishe ni wallahi."
Can k'asa-k'asa na ji tana fad'in." To na gode sosai sai da safe." Sai ta kashe wayar. A sanyaye na ajiye tawa a saman cinyata jikina duk ya mutu Hajja kuka take yi da gaske dalilin da ya sanya ma kenan ta katse wayar da sauri. Sai kawai ni ma na ji ruwan hawaye ya ciko idanuwana wani kutittiran abu ya tsaya mini a wuya. Lallai matar nan ta wuce ta nemi alfarma a wurina na tsaya yin jayayya da gaddama ba zata cutar mini da yara ba. Wannan maganar zuciyata ke ta nanata mini. ........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida

Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 n

*93*
"Maganar
Hauwa ai bata shafe ki ba Amina don haka babu ruwanki wannan tsakanina da ita ne kawai tunda ta ce ba ta ji to sai mu zuba ni da ita shege ka fasa."
Ya fad'a yayin da yake sake janyo ni jikinsa. Na janye a hankali na ce."Ya zaka ce babu ruwana bayan kai ma kasan a saboda ni da abinda ya shafe ni kuka samu sa'ba ni har da rabuwa ai gaskiya ba zan iya yin shiru ba domin abinda ka yi bai dace ba. Kamar yadda take ha'kuri da kai ya kamata ace kaima ka yi hakuri da halayenta ai zaman auran kenan."

"To yanzu ya ki ke so ayi?"
Ya fadi hakan cikin 'kosawa da maganar domin gabad'aya yanayinsa ya nuna ba itace a gabansa ba.
Na ce." Ka mayar da ita tunda ciki ne da ita sanin kanka ne a musulunci babu kyau sakin mace da ciki, kuma idan Hajja ta ji hakan ranta ba zai yi mata dad'i ba gaskiya."
"Ai ita Hauwa ba ta duba haka ba Amina, kuma cikinku wallahi kada wadda ta kuskura ta gayawa Mahaifiyata akan hakan rai zai 'baci."
"Ai kai zaka gyara matsalar gidanka kafin ta fita waje idan ba ka so Hajja ta ji abinda ka yi sai ka yi gaggawar gyara kwabar da ka yi."
Ya 'bata rai yana fad'in." Kina so ki ba ni umarni kenan?"
"Ba umarni ba ne ban isa ba, shawara ce nake ba."
"To ba zan d'auka ba har sai kun je ke da ita kun bawa Maryam da 'yar uwarta ha'kuri akan abinda ku ka yi musu. Na rashin kyautawa."

Ido na zuba masa ina kallonsa da mugun takaici.
Na gyada kaina tare da janye idona daga kansa ban ce komai ba..
Sai ya cigaba da ce wa." Wannan shine kawai, ki ja ta tunda tare kuke kulle-kullenku sai ku je ku ba su ha'kuri domin mun yi magana da Nabila ce wa gobe za ta koma jos, to kafin ta tafi din sai ku gyara kuskuranku, ni kuma sai na mayar da ita dakinta."
Na juyo fuskata a d'aure " Wannan kuma shine ba zai yiwu ba, idan hakurin da ka ba su bai isa ba, shikkenan don Allah ka cikashewa Hauwa sauran igiyoyinta da suka rage, idan hakan ma bai yi maka ba sai ka had'a har da ni gabad'aya."
Ya ce." To kada ki sake yi mini magana akan abinda ya shafi tsakanina da Hauwa, ba ke ki ke auranta ba, ni ne babu ruwanki wannan shine maganarmu dake ta k'arshe akanta."
Na dinga kallonsa zuciyata na sake suyuwa da kutun takaici da b'akinciki. Wannan wani abu ne da zai yi masifar wahala a ce Hauwa ta je ta bawa Momi da Nabila ha'kuri saboda iya zaman da na yi da ita na gane cewa macace mai mugun girman kai da kifad'i, ga taurin kan tsiya, bai shirya kwantar da rikicin ba, domin da ya shirya mutuwar matsalar ba zai 'bullu da wannan abinda ya san lallai da wahala ya yiwu.

Jin an kira shi a waya ya sanya na tashi na fita daga d'akin ba tare da na sake cewa komai ba, matsalarsu ce can ta family iyakacina shawara, kuma ni ban tura Hauwa cewa ta yi abinda take yi ba, akan kanta take yi saboda wata manufa tata da kuma masifar kishi, duk wanda zai zarge ni da hannu akai ya d'auki hakkina. Ba zan sake cewa masa komai ba.

Bai kwana a gidan ba a ranar sai washe gari wajen daya da rabi ya shigo cikin kayan shan iska da cazbaha a hannunsa ga dukkanin alamu daga massalaci ya fito mabiyin sunnah ne sosai da zazzafar akida da rashin son bidi'a da yawa. Bai fad'a ba amma tuntuni na gane ce wa mugun dan izala ne tunda yawanci abokanshi larabawan nan na madina duka 'yan ahalissuna ne.
Muna falo duka a zaune ya shigo ya d'an tsaya ana gaisawa ya amshi ta kowa a d'an sake. Ina kallon Hauwa bayan sun gaisa ta tashi a sanyaye ta shige daki. Sai na ji wani iri a raina, na yi shiru tare da yin k'asa da kaina ina jin suna ta labari da Baba Tabawa kamar yadda suka saba. Ya jima a tsaye a wurin suna magana ban tofa tawa ba. Kafin ya haura samansa.
Baba Tabawa ta juyo tana kallona da wani yanayi na alhini da damuwa ta ce." Irin wannan matsalar nake ta guje muku faruwarta Amina, rayuwar nan gabad'ayanta 'yar ha'kuri ce, shi namiji yana fa da wani irin iko da damar da Allah bai bawa mace ba, yakan iya yin komai ya kwana lafiya amma ita mace za ta yi abin ya zame mata matsala gagarima, ita wadda kuke ta ha'kilon akanta tana can hankalinta kwance mijinta ya kar'bar mata rigimar tunda ai kun had'e mata kai, ai ta fi ku wayo ta kuma fi ku shekaru da gogewa ta yaya ko tana da laifi zai gani bayan koyaushe cikin nuna alherinta take. Ki duba ki gani cikinku babu wanda ya fi kusanci dashi sama da Hauwa amma yau an

wayi gari tana wasan 'buya da shi. Shi kuma ko a jikinsa bai damu ba, ya kamata a ce ku nemi sulhu ita Hauwa ta kar'bi kuskuranta tunda a bayyane yake ta yi ba daidai ba."
Murmushi na yi irin na rashin sukuni na ce." To Baba Tabawa ya za a yi ne, mun jima muna magana dashi jiya da daddare abinda ya tsiro dashi ne nake ganin da wahala ace ya yiwu nasan Hauwa sai dai a rabu akan ta je ta ba su ha'kuri abinda ya ce kenan muddin tana so su daidaita ta je ta bawa Momi ha'kuri da k'anwarta Nabila akan zagi da 'kaharun da ta yi wa iyayensu, ni kuma nasan halin taurin kanta da mugun kifad'i."
Ta gyada kanta cikin damuwa tana ce wa." To ke dai ki yi takatsantsan sosai, amma a shawarce ina ganin ta bi umarinsa kawai domin zahiri mijinku ba irin wanda ake tursasawa ba ne ko kuma mace ta juya shi.
Na ce." Mu dai ba za mu juya shi ba. Amma ai matarsa da yake tare mata fad'a juya shi take yi kamar waina a tanda idan ba haka ba menene dalilin da zai sanya ya saki matarsa a kanta uwar babban dansa namiji kuma yar uwarsa. Baba Tabawa ki dubi lamarin nan fa da kyau!"

Baba Tabawa ba ta kai ga magana ba kiransa ya shigo wayata da take ajiye a gefana. Ina d'agawa ya ce." Ki zo yanzu." Bai bari na ce komai ba ya datse kiran. Na yun'kura na tashi da wayar a hannuna ina fad'in.'' Baba bari na sauko sai mu cigaba da tattauna maganar da muke yi."
Ta ce." Shikkenan a sauko lafiya."
Ina hawa saman gabana ya fadi ganinshi zaune daga shi sai karamin wando na ciki ya cire kayan dake jikinsa. Kallo daya na yi masa na d'auke idona domin lokaci guda na fahimci menene a cikin kwayar idanuwansa. Gabana bai daina bugawa ba har na isa inda yake zaune. Na zaune zuciyata cike da zullumi da damuwa. Ya ce." Za mu sake gaisawa ko?" Kallonsa na yi cikin nauyin baki na ce." Ai mun gaisa da ka shigo.
Ya kamo hannuna yana duba yatsun kafin ya rintse da nasa ya hade yatsunmu wuri d'aya a hankali ya ce." Wata kalar gaisuwa na zo miki ta mussaman kamar yadda kike ta mussaman a wurina."
Shiru na yi tare da yin k'asa da kaina. Wai dadin baki zai yi mini da kalamai saboda yana so ya kwanta da ni, tun jiya na gama gane inda ya dosa.
Na fara jin cikina yana murd'ewa domin ban san ta yadda zan sanar dashi cewa cikin nan fa ya sake ficewa ba.
"Kuna da abinci ko, domin ina so na cika cikina kafin na wani lamari mai girma ya faru a tsakaninmu."
A hankali na ce." Da abinci Baba Tabawa ta yi sai dai ba irin wanda kake so ba ne jallop din taliya ne da kifi.''
Ya d'an sake rintse hannuna dake cikin nasa a karo na biyu yana shafa mini tsakiyar hannu
ya ce." Gaskiya kam ba irin nawa ba ne, amma in dai da zafi a ba ni zan iya ci a haka."
Na ce." Da zafi mana tunda a kula yake." Hannuna nake ko'karin cirewa daga cikin nasa ya rike yana fad'in." Wai ke ba kya yin irin 'kunshin nan ja da 'baki zai yi mini kyau domin kina da kyawun fata ina so a dinga yi mini."

Shiru na yi. Ba tun yau ba na fahimci yana son lalle sosai, ni ce dai ban mayar da hankali ba, amma na lura matarsa Momi tana yawan yi. Amma henna ake yi mata a kafafu da yatsun hannuwanta. Ya ce" Akwai wata yarinya dake yi wa Maryam zan sanyata ta turo muku ita sai ta yi muku."
A takaice na ce." Sai ta zo. Ya bi bakina da kallo yana lumshe Ido. Wani irin yanayi na ji a jikina amma nan da nan na shiga taitayina domin na fi kowa sanin cewa matsala ce kwance-kwance. Cikin 'yar damuwa na ce." Na kawo maka abinci ne?"
Ya girgiza kansa alamun a'a. Na ce." Saboda me?"
"Ke kadai za ki iya gamsar da ni yunwar cikina."
Na yi shiru dai. Ina jinsa ya matso sosai tare da janyo ni jikinsa yasa hannu a dokin wuyana yana tatta'ba wajan da ya zama guru-guru kafin yasa baki ya sumbata. Shi kuma wuyana yana bashi sha'awa ko sunna muke yi ya dinga sumbatar wurin kenan har dasu sanya harshe.

Ya dora hannuwansa biyu duka a saman kirjina. Ajiyar zuciyarsa na ji a saitin kunnena. Ganin ya fara ki'dimewa sai na dan ja baya tare da jan hanci domin na ma kasa cewa komai sai zare ido nake yi.
Ya sake matsowa yana fad'in." Menene haka, yaushe rabon ma da na nemi wani abu Hajiya ko ba ki yi kewata ba ne.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne 1k akan telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*94*

Na ce." Ba haka ba ne, kawai dai ina so na gaya maka ne cewar ba ni da tsarki."

Sai ya yi sakato yana kallona har ya so ya ba ni dariya domin wata kala ya zama kamar wani sakarai. Na yi kasa da kaina na ji yana cewa." Ina ce 24 ga kowane wata na bature kike yin al'ada ko ba haka ba ne, yau nawa ga wata?" Ya fad'i maganar yana tsatstsare ni da ido. Ban dube shi ba na ce." Yau shida ga watan aprilu."

"To mai ya kawo jini kuma?"

Shiru na yi domin kuwa zahiri ba na so na yi masa k'arya amma da sai na ce ai lokaci ya kan canza sa'i, da lokaci mussaman idan shekaru suka tura.

Tambayarsa ya sake maimaitawa idonsa a kaina. Cike da shahada da kundubala na ce." Dama ina so na gaya maka ban san yadda za ka kar'bi lamarin ba, amma ni Allah ne shaidata, shine kuma zai tsaya mini a ko'ina, wallahi shekaran jiya cikin da nake d'auke da shi ya fita. Amma na alak'anta faruwar hakan da wannan rikicin da muke ciki, alhamdulillahi babu wata matsala domin Hauwa ta sanya Masa'udu ya sayo mini magunguña masu kyau sun taimaka mini k'warai wurin wanko mini mahaifata."

Lokaci k'ankani yanayinsa ya daidaita babu wani rausaye-rausaye da lumshe-lumshen Ido irin na fitina, zahirinsa ne ya bayyana ya 'kura mini idonsa da wani irin yanayi na mussaman tattare da shi.

Kasa jimirin kallonsa na yi sai kawai na yi 'kasa da nawa idon cikin zuciyata ina fad'in 'Duk abinda za ka yi, ka yi wanda ya fi shi a baya kaddara ce.

'Dakin ya d'auki shiru na tsayin mintina bai tanka mini ba amma a jikina na ji cewar har yanzu bai cire kwayoyin idanuwansa daga kaina ba.

Cike da ko'karin ture rauni da kasalar dake ko'karin dabaibayi ni na dago idona. Karaf idonsa ya shiga cikin nawa, gabana ya fadi ganin cikowar k'walla a dukkanin kwarmin idonsa don sauran kad'an ma ta fara tsiyaya.
Gwiwa ta sage cikina ya sake murdawa. Cikin gaggawar na sake yin k'asa da kaina ban yadda na sake kallonsa ba domin ji na yi gabad'aya na sare lamarin har ya kai a ce za a zubar da kwalla. Na san a yanzu abinda ya fi buri da buk'ata bai wuce ganin gidansa cike da yara ba. To ni ba budurwa ya aure ni ba, balle ya ce, sannan kuma shekaruna sun yi nisa dukda dai ban wuce haihuwar ba, bayan haka kuma ni dashi muna da matsala wadda ya taketa da k'afafunsa na kuma yi hakuri na bi shi a yadda yake so. Ba ni da niyyar sake zubar masa da ciki tunda alkawari na d'auka tun lokacin sulhunmu da Baban Saude. Idan zan samu ciki ya kasance duk yaron da zan haifa yana da matsala zan jure dalili alkawari da rantsuwar da na yi wa Baban Saude Allah ne mai yin yadda ya so.
Kuma wallahi ni kaina na ji b'akincikin fitar cikin to don babu yadda zan yi ne kawai ya sanya ni ha'kuri ne tare da barwa Allah ikonsa. Ba ni jin ko da wasa duk irin rikicin da za mu yi dashi zan sake yun'kurin zubar masa da ciki da gagan domin tun farkon fari na gane hakan lamari ne mai mutukar hadari daka iya janyo babba matsalar da za a yi wahalar shanyo kanta dalili na ci wuya 'barin da na yi sakamakon shan kwayar zubar da ciki shiyasa gabad'aya lamarin ya fice mini daga rai na ajiye a zuciyata cewa zan haihu idan Allah ya kaddara mini koda yaran za su kasance masu rauni ta kowace siga.

Gyaran muryarsa ya dawo da ni daga dogon tunanin da na tafi. Dubansa na yi sai na ga babu kwallar gogeta ya yi ko mayar da ita ya yi Allah ne masani.
"Ta shi ki ba ni wuri kawai Amina, Allah Ubangiji ya yi mini sakayya." Wannan maganar ya furta mini babu sukuni a tare da shi.
Ban ce masa komai ba kuwa na tashi na kama hanyar fita daga d'akin kamar yadda ya buk'ata. Allah ai al'musauwiru kuma da zuciyar bayi yake aiki.
Jikina gabad'aya duk a sanyaye ban san kuma mai ya taka ba tunda zahiri yanayin da ya shiga ya nuna mini cewa ya ji zafin abin.
Bayan kwanaki biyu gidan na mu ya kasance kamar kufai. To babu motsin yara shiru. Hauwa kuma ta tsiri zaman d'aki sai na yi, na yi da ita ta fito falo ta'ki. Sai yamma muke zama ni da Baba Tabawa mu d'an yi hira. Shi kuma maigidan tun shekaran jiyan da ya fita bai sake leko mu ba.
Baba Tabawa tana kicin domin d'ora sanwar dare na fito falon da waya a kunnena.
Bikin Yusura ne ya tashi kuma abinda ya kawo tsaiko a wancan lokacin balagorun da saurayin ya yi libiya domin neman kudi dalilin da ya sanya iyaye suke ce a bari ya dawo sai a d'aura auran tunda duk gidana. Mun gama magana da ita akan kada na ga ta sayi ko cokali domin tun da aka kawo kudin nake jadadda mata. Wancan karon ma na sanyata ta yi amfani da maganin sanyi hakan ba zai 'ki ba tunda ai 'ya macace, ita kuma duk inda take 'yar gyara da kula ce. Kuma koyaushe ba'a rabata da maganin sanyi domin shine tushen gyara aure da lalatashi. Garkuwar mata itace mai

magunguñan Islamic din da na aminta da ita, dukda ita Hauwan ce ta had'a ni da ita, amma dalilin yawan sayan kayanta da nake yi ya sanya muka yi sabo da ita sosai. Duk wani nau'in magani na gyaran mace tana sayarwa masu kyau da inganci. Na ce ta sake yi mata magana akan ta hadawa amaryar set din amare kamar dai wancan karon zata hada mata magangunan sanyi da na gyaran nono sannan ta kuma yi mata budurwar kaza da sauran maganin gyara idan sun gama zan tura mata kudin daga nan, in sha Allahu 08089965176 duk wata 'ya mace da take neman sahihan magunguña masu kyau marasa cutar da GARKUWAR jiki to ta nemi GARKUWAR MATA domin kuwa kayanta duka babu na kaico ana samun biyan buk'ata.

Bayan mun gama maganar sai na kashe wayar na nufi kicin domin anan nake jin motsin Baba Tabawa na sameta tana ta buga sakawara a turmi. Na ce." Sannu da aiki Baba." Ta juyo da sauri tana amsawa. Na ce." Baba ko dai a samo miki wadda za ku dinga aikin nan tare, dukan sakawara na mai k'wari ne."
Tana dariya ta ce." Ni ma da kwarina ai, kuma aikin duka duka guda nawa yake. Yara ba anan suke cin abinci ba, ku biyu ne fa sai ni ta uku sai Masa'udu sai masu gadi biyu shikkenan fa, to sai kuma mai gayya mai aiki idan ya shigo gidan shi ma kuma sa'i da lokaci ne.
"Na ce." Hakane amma duk da haka za a cigita  wadda za ta taimaka miki koda da wanke wanke da shara ne ke kuma sai ki ji da girkin ko.''
Ta gyada kanta tana fad'in." To hakan ya yi babu lefi, yau na ce bari na yi sakawara an kwana biyu ba a yi ba. Na ce." Hakane kin ga ma tana daya daga cikin abinda maigidan yake so  bayan towon da kike masa." Tana bud'e leda ta ce." Ina kuwa fatan Allah Ya sa ya shigo gidan yau." Na amsa da amin a takaice kafin bar kicin din jin alamun motsi a falon.
Khalil ne tare da Usaina sai wata matashiyar budurwa da bata haura shekaru ashirin da biyar ba.
Rige-rigen gaishe ni suka fara yi har da tsugunawa "Mama ina yini." In ji Khalil na amsa ina dariya tare da nazartarsu yaran suna cike da walwalarsu da annushuwa gasu nan cikin suttura mai amince. Itama ta tsuguna "Mama ina yini." Usaina kenan. Dariya ta kama ni na ce." Ina yini Usai ina Hassana da Minal" Ta tashi tsaye tana ce wa." Suna can gida." Khalil ya ce. Momi ce ta ce wai ga mai lallan da take yi mata...

Littafin kudin aure na kudi yar uwata kada k8 karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na ce." Aikuwa ka ce mata mun gode sosai." Suka juya za su fita sai na ce." Kai Khalil dawo ku shiga ku gaida Mamanka mana." Ya ce." To. D'akinta suka nufa tare da Usaina tana bin sa zugwi-zugwi a baya. Na sauke ajiyar zuciya bayan shigewarsu na juyo kan mai lallan cikin nutsuwa ta gaishe ni na amsa ina fad'in." Wane iri za a yi mana ja ne ko baki?"

Tana fito da kayan aikinta daga cikin wata 'yar jaka ta ce." Duk biyun Ina yi wanda kuke so za a yi."
Na ce." To a yi mini duka ja da bakin. Amma dai ba na son dogon zama. Ta ce." In sha Allah daga nan zuwa magriba komai ya kammala."
Khalil ne ya zo ya gifta ni yana goge fuska. Da sauri na ce." Kai menene ." Bai ce mini komai ba ya wuce yana dafe idonsa. Kawai na ji fashewar kukan Usaina cikin gwarancinta tana ce wa." Mama ta dake shi a fuska."
Da wani irin yanayi na ce ." Mai ka yi mata?"
"Ba komai." Ya fad'a da sauri ya kama hanyar fita kamar ma a tsorace yake Usainar ta bi bayansa itama da sauri.
D'akin na shiga na ji motsinta a bandaki tana ta kakarin amai. Can na bita sai da ta gama tukkuna ta wanko fuskarta ta fito koda ta gan ni a tsaye a bakin kofa ba ta ce mini komai ba ta nemi gefan gado ta zauna. Laulayin ne ya dawo mata sabo da kuma hatsaniyar nan da muke ciki gabad'aya duk yanayinta ya canza ga wani uban haske da ta yi fau sai wasu k'ananun kuraje da suka feso mata a fuska.
Na ce." Wai ba ki da lafiya dama Hauwa."
Tabe bakinta ta yi kafin ta girgiza kai ta ce." Amai ne ya takura mini wallahi cikin 'yan kwanakin nan, amma in banda shi babu abinda ya dame ni."
Na gyad'a kaina a sanyaye na ce." Allah Ya bada lafiya." A takaice ta amsa da Amin.
Na ce." Khalil ya fito yana kuka Hauwa ba kya neman zaman lafiya ko, kin fi kowa sanin abinda mutumin nan ya tsana a rayuwarsa a daki yaran nan mussaman shi Khalil din daga gaisuwa kuma sai duka fisabillahi , ai ba shi ya yi miki ba."
"So na ke a yi ta take ai, shiyasa na dake shi. Ni ma ai iyayene suka haife ni. Ya dake ni a fuska kwanaki yanzu kuma yana dukan zuciyata da iyakacin karfinsa. Bai isa dai ya canzawa towo suna ba."
Shiru na yi Ina nazarin maganarta kafin na ce." Duk wannan bai ta so ba, za ki dasawa yaron nan k'iyayyarki da jin tsoronki a cikin ransa. zai kara yin nesa dake tunda tsakaninku duka ne da kyara da hantara, don girman Allah ki daina."
Hannu ta daga mini sai kuma hawaye suka k'wace mata ta ce." Kin san irin rad'adin da nake ji a zuciyata kuwa Amina ? wai Yaya Tajo shine yake fifita wata bare wadda ba su had'a dangantakar komai ba akaina. Na haihu dashi Bata haihu dashi ba. Jinina ne shakiki. Ita kuwa a duniya suka had'u, amma ya tozarta rayuwata a kanta. Wallahi har na mutu ba zan yafewa matar nan da alhalinta ba."
"Kai! Innalillahi! don darajar Allah Hauwa maganar nan ta mutu haka na rantse da Allah ta ishe ni. Ki gyara tsakaninki da shi kawai ki daina duba wata dangantaka namiji ne za ki ga abinda ya fi haka fa."
Shiru ta yi ba ta ce komai ba, na ce." Ga mai lalle ta zo za ta yi mana, ki fito falo."
Ta dube "Kin ga na yi kama da wadda za ta yi wani lalle yanzu?"
Na ce." Kwarai kuwa, ai ke ya kamata ma ki yi kitso da lalle domin jan hankalin mijinki ku daidaita har ya janye abinda ya ratsa tsakaninku."

Ta ja tsaki tare da gyara kwanciyarta tana fad'in." Kada Allah Ya sa ya janye wallahi babu abinda zan yi, ai ke ce matar gida.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya

07012621175
Register 8000 ne kachal
*95*
Na gyad'a kaina ba tare da na sake yin wata magana ba na juya na fita daga d'akin gabad'aya zuciya sam babu dadi, abin nata kuma ya fara ba ni haushi ya daga gyara kayanka sai ba'kar magana. Ai duk wanda ya sayi rariya ya san za ta zubar da ruwa. Ni ban ce Hauwa shigar rigima ba domin tun lokacin da na ga ta dage tana ta tsalle akan hatsaniyar nasan lallai da akwai abinda zai faru.  Ta sha gaya mini ita ta gaji da auran to yanzu kuma an sake ta tana kuka. Ni tausayinta ma nake ji wallahi ga ciki ga rashin zaman lafiya da miji dalilin da ya sanya kenan nake tausarta ta yi hakuri akwai takaici kwarai da gaske da ciwo namiji ya nuna baka da wani amfani a wurinsa domin dai sakin da ya yi mata ko a kwalar rigarsa bai damu ba ya dasa mata k'unci yana gefe yana cigaba da gudanar da rayuwarsa. Wadda take yi domin ita tana can hankalinta a kwance  mijinta yana neman hanyar da zai faranta mata da tun farko ta yi amfani da shawarwarina da duk hakan bai faru ba  ta lallaba ta zauna a dakinta.
Yarinyar ta iya lalle sosai tana da zane mai ban sha'awa ganin kamar ta d'auki mai wahala da jinkiri ya sanya na ce ta takaita domin ba ni son zama shine dalilin ma da ya sanya ban fiye yin k'unshin ba.
Baba Tabawa ta kammala aikinta ta fito ta zauna a falon muna hira jefi-jefi har yarinyar ta kammala tsaf ta had'a kan kayanta. Na ce." Ai kina da acct ko?"
Ta ce." E, ina dashi amma Momi ta ce da ni kada na kar'bi komai."
Cike da mamaki na ce." Saboda me?" Tana murmushi ta furta." Da farko antina ce take mata lalle sai ta yi aure ni ma dama tana koya mini shine na kar'bi sana'ar duk k'arshen wata nake shigowa cikin estate din nan naku akwai wad'anda nake yi wa bayan Momi din. Mun saba k'warai da ita ta yi wa antina komai haka zalika ta samawa babban yayanmu gurbi a daya daga cikin shagunanta dake garin nan, gashi nan har ya yi aure shekara daya kenan matarshi ta haifi mace ya sanya mata sunan momi din wato Maryam muna kiranta da  Sahiba."
Da murmushi a fuskata na ce." Duk da haka dai ai ni ma alheri zan yi miki ganin irin yadda ki ka b'ata lokaci wurin yi mini ado da zananan henna mai kyau, shin ko ba kya so mu saba ne?"
Dariya ta yi kafin ta ce." Kai anti wannan ba komai ba ne akan wanda nake yi don na ji kin ce na takaita ne shiyasa amma da wanda zan yi miki sai ya fi wannan tsaruwa."
Na ce." Wannan din ma ya burge ni sosai na gode miki, amma ai ko turare kya kar'ba ko."
Ta yi kasa da kanta tana murmushi. Ni ma murmushi nake yi can kasan zuciyata kuma ina tunanin idan har mutane za su dinga yabonka tun kana raye tabbas babu abinda zai hana ka sha'kar rahamar Allah idan ka gushe! wato ita dai Momi ko'ina alherinta zagayawa yake yi duk wanda ala'ka ta had'aka dashi muddin ya santa to alherinta zai fara gaya maka.

Muna nan zaune muna hira da ita budurwar wadda take gaya mini sunanta Lad'ifa iyayenta yan asalin jalingo ne aiki ya kawo mahaifinsu nan abuja amma k'aramin ma'aikaci ne..
Ta duba agogon da yake tsintsinyar hannunta na dama wanda nake hasashen tana d'aura shi ne domin duba lokaci a sa'in da ta d'aurawa mutam lalle da kwance shi.
Ta ce." Yanzu sai a cire tunda ya samu awa biyu cikakku. Dama dalilin da ya sanya ban tafi ba kenan.. ta d'auko wata leda babba da cokali mai dan fadi daga sama cikin nutsuwa ta fara cire lallen kafin ta d'aye salatif din zanen ya fito d'au ya yi bala'in kyau da kamawa. Baba Tabawa fadi take yi "Ashe haka kike da cin lalle Amina amma ba kya damuwa da yi."
Na ce." Duk da haka dai ai lallensu daban yake suna yi masa hadi na mussaman."
Da kaina na cire na hannun ya tafi da ni sosai nan da nan na ga ba dawo mace har ina jin dadin duba hannuna. Na ji tana ce wa." Sai gobe zai sake fitowa sosai." Tsaf ta goge mini kaf ta shafe duk inda lallen yake da wani abu sannan ta sake had'a kayanta a karo na biyu. Baba Tabawa da kanta ta d'auko mini takalmin da da nake amfani da shi a d'akina ta kawo mini na sanya na tashi ina fad'in.'' Ladifa alwala ai ta zama dole da fatan babu matsala ko." Tana murmushi ta ce." Babu matsala anti."
Kai tsaye d'aki na wuce na had'o mata Turaruka da sabulai.
Fitowa ta yi daidai da lokacin da ya shigo yana daga bakin kofa suna magana da yarinyar kamar sun d'an saba da juna ko da yake shi din ba ma'abocin shariya ba ne idan yau kuka hadu to zai mu'amulanceka kamar kun yi shekara da sanin juna, mutum mai sau'ki hali da nuna shi ba wani ba ne a rayuwa.
Wannan dabi'un nasa na zahiri sune suka danne ba badi'ini wanda mu da muka dangance shi kuma mafi kusa dashi yake yi mana. Amma kaf jama'a da ma'aikatansa yana mu'amulantarsu ciki sau'ki babu wata izza da nuna ni wani ne. Abinda anti Yagana take fad'a kullum kenan domin ita kanta ladabi yake yi mata ko magana suke yi baya iya had'a ido da ita wai ai yayata ce wasu lokacin har anti Yagana yake ce mata kamar yadda nake kiranta abin ya yi ta bani takaici da b'akinciki. Makirci sai kace babbakakken dan duniyar da ya gaji da yawon bariki kaf ya saye mini dangi har da Baban Saude domin sai da ya san yadda ya yi ya 'kulla abota da shi mai karfi. Amma nasan Baban Saude mutum ne mai tsinkaye da hangen nesa kuma ba zai ta'ba take gaskiya ya d'auki karya ba idan duk duk duniyar nan za a ba shi yana da taurin kai da ra'ayin rikau!

Ledar hannuna na mik'a mata ina cewa "Ki gaishe da mutan gidan, tunda kin ki kar'bar kudi ga wannan sai ki yi amfani da su, na gode kwarai."
Ta kar'ba tana godiya sosai kafin ta kama hanya ta fita cike da nutsuwa. Baba Tabawa ta wuce dakinta itama. Sai mu biyu a falon na daure na ce." Barka da shigowa."

Don girman Allah kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

A takaice ya amsa kafin ya nemi hanyar matattakalar samansa. Ban yi kasa a gwiwa ba na bi bayansa. Ya shiga bandaki nasan alwala zai yi ya fito yana gyara hannun rigarsa dake tattare. Kallo daya ya yi mini ya kama hanya zai fita na ce." Idan babu damuwa Ina son magana da kai."
Bai juyo ya dube ni ba ya furta." To, bari na dawo daga massalaci." Ya fice a gaggauce.
Na samu gefan gado na zauna babu wani karsashi a tattare da ni, nasan da ban yi masa magana ba, bai zama lallai idan ya fita ya dawo ba, shigowar nan ma nasan ya yi ta ne akan dole domin sanin halin da muke ciki. Idan yana irin wannan nuk'ufurcin da d'aukewar kai wani irin damuwa nake shiga mara dad'i don ni kuma gaba damuna take yi idan na fara ma bana iyawa gwara kawai a yi fito na fito a shirya amma ba ni son kisan mummu'ke da ba'kin rai.
To ban yi tsammanin amsa min din da ya yi ta bogi ba ce sai da naga har an yi Isha'i ta shige bai dawo gidan ba ya barni zaune a inda ya bar ni ina dakon shigowarsa. Bakwai saura ya fita yanzu gashi takwas har da minti ashirin na samu kimanin awa d'aya da wani abu zaune zuru a d'akinsa.
Na tashi na sauka kasa raina a dagule haka kawai nake kasa jimirin jure shariyarsa akaina duk dauriyata gazawa nake yi, kuma da na ce ina son magana da shi zahiri ko ya dawo din wallahi ban san abinda zan ce masa ba.
Waya na d'auka na kira shi, bai yi jinkiri ba kuwa ya daga yana tambayata menene. Daburcewa na yi kafin daga bisani na daure na ce." Ka zo."
Ya ce." Akan wane dalili."
Shiru na yi ina d'an tunani sannan na ce." A lissafin da kake yi yau kwanan wanene a cikinmu?"
Kai tsaye ya ce." Kwana kamar yaya."
Na ce." Kwanan girki mana, wacece take da kai?"
Ya ce." Momi ce take da ni ma, saboda itace nagartacciya matar da take gudun fushina ita nake ganin zan iya kwanan aure da ita, domin zahiri da bad'ininta babu mugunta ko zagon kasa balle zalinci a tare da ita."
Shiru na yi maganarsa na dukan kaina. Na daure na furta." To mai kake nufi?"
"Ba na nufin komai, kawai dai ya kamata a ce na yi nesa daku dalili ban san menene a zuk'atanku ba ke da ita Hauwan mai aikawa a sayo miki maganin wankin mahaifa."
Maganar ta yi mini nauyi sosai, dama nasan abinda yake ta sa'barsa kenan. Na ce." Ai ba haka kawai ta aika a ka sayo mini maganin wankin mahaifa ba sai da dalili, idan ma kana ganin da hannunta a wannan case din to ka d'auki hakkinta wallahi."

"Ita din mutuniyar arziki ce kenan?" Ya fad'a da izgili." Na yi shiru ban bashi amsa ba domin yadda ya fadi maganar ya nuna mini cewar a fusace yake.
Jan tsakinsa na ji kafin ya datse kiran. Na cire wayar daga kunnena raina a kuntacce na tashi na shiga bandaki domin gyara jikina.

Da kyar na iya cin abinci duk kuwa da dokin sakawarar da na yi amma takaici bai barni na ci da yawa ba. Hauwa kam ko dand'ane ba ta ce ba a daran sai da Baba Tabawa ta yi mata fatan wake da manja da kifi ga uban attaruwun da ta ce a zabga mata saboda yanayin bakinta.
Sai bayan goma na dare tukkuna muka yi sallama kowa ya shiga domin ya kwanta.
Lokacin kiran Hajja ya shigo wayata can saman dirowa romat na d'auka na rage murya domin koda na shiga d'akin kallo na kunna domin idanuwana gabad'aya a soye suke da zallan b'acin rai da damuwa
Na shiga zullumi da nazari sosai a lokacin da na ga kiran Hajja domin sai nake tunanin ko ya sanar mata da wata magana ne. Yanayin yadda muka gaisa da wasa da dariya ya sanya na dan ji sanyi a raina sosai ta yi mini tambayoyi masu cike da hikima irin ta manya ni na na bata amsa cikin hikima ban yarda na sanar da ita akwai matsala ba tunda bai gaya mata ba, to fadarta daga bangarena takan iya janyo mini matsala babba......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego
Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer

Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma company yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*96*
Ta ce." Ga Yusi dai muna tare dashi anan falo duk ba mu kwanta ba, Kamulu kuma ya ce mini zai shiga cikin gari can gaba da gidanku rijiyar zaki ya ce mini idan ban manta ba an gayyace shi bude wata sabuwar makarantar islamiyya ya ce mini zai kwana a gidan Gwaggo da safe sai ya wuce can din."
Murmushi na yi a tsanake na ce." To shikkenan Hajja, Allah dai Ya saka da alheri na gode sosai, Allah Ya kara lafiya da nisan kwana."
Ta amsa da Amin Ya Allah. Kafin ta bawa yaron wayar na ji maganarsa yana fad'in." Mama barkanmu da dare.
Na ce." Barkanmu dai Yusi ya kuke?" Ya amsa da "Alhamdulillahi Mama." Shiru ya biyo bayan maganarsa. Gabad'aya tunda abin nan ya faru yaron baya sakewa da ni. Kamalu ne ma ya kira ni a waya shi ma sau daya sai ka ce wad'anda aka yi wa wata hud'uba akaina. Kai na girgiza a hankali na ce." To tunda ba ka da abin cewa sai an jima ko.".
Yana 'yar dariya ya ce." Mama kenan, na yi shiru ne ai ina sauraranki ko da abinda za ki ce mini."
Na ce." Da yake ni ce sarkin k'orafi ko?"
Shiru ya yi bai ce komai ba, amma ina jin sautin murmushinsa. Na ce." Malam kashe waya ka bawa mai ita."
Da sauri ya amsa da "To Mama." Amma ban ji ya kashe din ba, nasan jira yake yi ni na fara kashe tawa.
Murmushi kawai na yi na ajiye wayar a gefena tare da sauke ajiyar zuciya.

Washe gari kiran wayar Baban Saude ne ya tashe ni da yake jiya na jima ban yi bacci ba idona ya soye da tsabar tunani tare da neman mafita. Wannan shine dalilin da ya sanya da baccin ya kwashe ni bai ajiye ni a kusa ba domin ni kaina tunda nasan ba ni da tsarki sakin jikina na yi sosai motsin kirki ba na so na yi.
Hannu na kyarma na d'aga wayar lokaci guda idona ya yi tarmazai wani irin yanayi na shiga na fargaba kiran wayar Baban Saude a irin wannan lokacin

yana da ala'ka da abubuwa da yawa. Walau mutuwa ko wata mas'alar domin kuwa nasan a cikinta muke
Muryarsa radau ya amshi gaisuwata ya dora da fad'in gani nan kan hanya domin kuwa daf nake  da shigowa garin abuja.
Na ce." Baban Saude ziyara za ka kawo mana kenan, ka gaya mini abinda ka ke so ka ci yanzu da kaina ma zan shiga kicin din na yi maka.
Ya ce." Ai ba abincin gidanki na zo ci ba Amina, ni ko da me ki ka sauke ni a wajena daidai ne."
A hankali na ce." To shikkenan Baban Saude Allah Ya sauke ka lafiya."
Ya amsa da Amin a takaice kafin ya kashe waya.
Na jima cikin nazari da tunanin dalilin zuwan Baban Saude a wannan safiya haka sai kace wanda ya kwana a hanya. Ashe ni da mutumin nan ba mu isa mu kashe matsala mu binne ta ba har sai ya dangatata da iyayena.
Gaza ha'kuri na yi na daga waya na kira shi. Matarsa ce ta daga har tana kiran sunana. Da sauri na daidaita yanayina muka gaisa a tsanake kafin ta ce." Yallabai din bacci yake yi ko a tashe shi ne?"
Na ce. "A'a kada ki tashe bari idan ya tashi sai ki gaya masa na kira."
Na ji tana fad'in." Yawwa gashi nan ma ya tashi can sama sama na ji maganarsa ban fahimci mai yake cewa ba na ji tana ce wa dashi Maman Yusuf ce." Na ji shi sosai yana fad'in.'' Amina." Ta ba shi amsa da e, ita ce ya ce ta bashi wayar.
Na ji dad'i da bai nuna mata a cikin rikici muke ba. Maganarsa na ji ta daki kunnena."
"Ya aka yi?"
Zuciyata ta yi wani zullo kamar za ta faso kirjina ta fito. Kalmar ''Ya aka ayi din nan tana yi mini ciwo kwarai da aniya, bayan yasan a cikin yin muke ni da shi.
Na daure na furta." Yanzu don girman Allah Baba menene amfanin kiran Baban Saude da ka yi ashe ni da kai  ba mu isa mu warware matsalarmu ba, mai ya sa har yanzu ka kasa yarda da ni."
"Ya za a yi na yarda dake Amina? ba ki d'auki hanyar ba domin kuwa duk yadda na so ganin cewa da ni dake mun zama abu daya kin ki ba ni goyon baya, 'kiri-'kiri ki ke nuna mini gadara da ikon akan yaran da ki ka haifa da namijin da ki ka fi so a duniyar nan. Na ha'kura na kyaleki duk da cewar nasan har yanzu zuciyarki na kewar wannan mutumin da ya riga ya gushe a doran duniya bayan da igiyoyin aurena a wuyanki. Tunda kin fad'a tun farkon fari soyayya ta gaskiya daya ce shi kuma ki ka bawa shiyasa ki ka fifita 'ya'yansa a kan nawa, zahirin kiyayya da rashin k'auna da kulawa kika nuna mini Amina
gashi ko kunya ba kya ji kina gwada fifiko da soyayya akan yaransa. Ni na yi ha'kilo na raba dare wataran ma da rana  idan abin ya ciyo ni, na yi ta ko'karin ganin na samar da k'wayayyaina a mahaifarki kina zubarwa saboda ni din kare na bai kai tsaiko ba. Mai yasa zan yarda dake kuwa Amina. Na tabbatar da cewa Hassana da Usaina ma Ubangiji Allah ne ya nuna miki ikonsa a kansu ke kam ai tunda suka diro duniya ba ki isa ki shafe babinsu ba. Za su rayu ko da babu soyayyarki."

Kaina ne ya dinga juyawa maganganunsa na ta amsa mini kunnuwana. Na rasa wadda zan d'auka a ciki na yi nazari. Wane irin zargi ne wannan da mugun bala'in kishi. Yaya Aminu ma da ba kowan kowa ba a duniyar nan musaki mai lalura har shi za a dinga yi wa wannan mugun kishi na bala'i. Zuciyata ta ce da ni wannan shi ake kira da "Kishin kushewa."
Ban ankara ba kawai na ji kittt! ya kashe wayarsa. Na ajiye tawa a saman cinyata kana na tallafe ha'bata tare da nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Da gaske shi din ya kira Baban Saude saboda yana zargin na sake zubar masa da ciki. Hawaye ne ya silalo saman kuncina, ni kam mutumin nan Ina ganin ni kadai ya tsana a cikinmu, gabad'aya ya ki bari na na huta a rayuwata.

Na kai minti goma ina nazari a cikin raina ba wai na fifita su Kamalu akan su twins ba ne. A a gane inda ya dosa a kan yaran ya sanyi ni kama kaina domin shi kusan duk rigimarsa akan su ne, idan na ce zan biye masa kamar yadda Hauwa take yin fad'a dashi akan abinda yake mana zuciyata zan sanya kunci shiyasa nake nuna masa tamkar yaran basa gabana. Amma Allah daya ne wallahi da tunaninsu nake kwana nake tashi a cikin raina, a duk lokacin kuwa da za su shigo mana nakan kasance cikin farinciki na yi ta kallonsu ina jin dadin ganinsu cikin kulawa har yanzu duk hasashe da zinden da Hauwa take akan matar ban hango wata tawaya ta cutuwa a tattare da yaranmu ba. Na farko a nutse suke shigo mana cikin tsabta. Su gaishe mu har da risinawa babu kiriniya irin ta 'kuruciya mussaman Khalil a nutse yake sosai, twins ne ma suke fad'a a tsakaninsu sai Minal da na ji uban wataran yana fad'in taurin kai ne da ita.

Cikin kasala na yi wanka ina ta nazarin hanyar da zan 'bullo da ita domin ko'karin ganin na kare kaina tunda ban san irin maganganun da ya tsarawa Baban Sauden ba, kuma ban san shi din da me yake tafe ba.
Ban yi wata kwalliyar kirki ba saboda babu nutsuwar yin hakan a tare da ni. Na gama shafa mai ina duba lallen jiya ya sake fitowa sosai ya bi fatar 'kafafu da hannuna ya kwanta abin ban sha'awa.
Zuciyata babu sukuni na fita falo muka gaisa da Baba Tabawa lokacin tara da minti takwas na safe ta kammala shirya abin kari tsaf har ta yi wanka. Na tambayeta Hauwa ta ce mini ba ta fito ba tukkuna.
D'akinta na nufa sai na sameta nad'e a cikin bargo tana bacci. Ban yi yun'kurin tashinta ba saboda nasan illar hakan na janyo kofar a hankali. Na dawo falon na zauna ina kallon Baba Tabawa daka can wurin daning tana gyarawa na ce." Baba mai aka yi ne yau."
Sai da ta d'ago ta dube ni kafin a tsanake ta ce." Kunun gyada ne sai kosai da fanke, sai na yi wa  Hajiya Hauwa Indomee kuma kamar yadda ta buk'ata."
Na ce " To kawai tsiyayo mini kunun da k'osan amma ba mai yawa ba.
Ta amsa da kulawa. Na janye idona daga wurin da take zuciyata na can tunani na tsinkayi maganarta ina d'aga kaina na ganta a tsaye ta miko mini

madaidaicin kofin da ta tsiyayo mini kunun kosai kuma ta ajiye mini shi a saman hannun kujerar da nake zaune .
Ban ce komai ba na sanya hannu na kar'ba sai ta zauna gefana jikinta a sanyaye.
"Na gama alamar akwai abinda yake damunki hajiya tun fitowarki na lura da hakan, ina yi muku addu'a tare da fatan Allah Ya iyakance muku wannan rikicin."
Haka kawai sai maganarta ta karya mini zuciya na ji hawaye sun cika idanuwana. Tunda nake shiga matsaltsalu na rayuwa da rikicin duniya ban ta'ba jin kewar mahaifiyata ba sai wannan karon da nake ganin karfi da dabarata sun yi rauni. Komai ya cakude mini na rasa yadda zan yi da rayuwata. A irin wannan yanayin ne ya kamata a ce na je kafadarta na d'ora kaina a kai, na yi kuka ta share mini hawaye ta kuma fahimce ni ba tare da ta kyare ni ba..
Hawaye suka tsinke mini dalili na kasa jimirin jure hana su gudana. Ina ganin kamar kukan ma zai sanya ni na ji sasaauci a cikin zuciyata. Duk da ban rayu da uwata na tsayin lokaci mai yawa ban shaku da ita ba, amma ina shiga tsananin tashin hankali da kewa a duk lokacin da na tuna cewa ba ta raye na tuna irin wahala da gwagwarmayar rayuwar da na fuskata gani a cikinta sau'ki sai daga Allahu rabbi..

Kada ki karanta littafin nan ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Anti Yagana uwa ce a makwafin Mamanmu amma bai zama tilas ta fahimce ni ba kamar yadda uwa take mayar da damuwa da kukan d'anta nata. Uwa ta kan kar'bi wahala da fad'i tashi akan dai duk rayuwar abinda ta haifa. Idan tawa tana raye a 'kalla ni ma zan ji sasaauci ta wani gefen zan je na gaya mata damuwata ta fahimci ni kuma ta ba ni shawarwari.
Cikin nashihun da Baba Tabawa take yi mini babu wadda na fahimta gabad'aya rauni ya yi mini 'kawanya  na ma gagara tsayar da hawayen dake karakaina a dakalin fuskata. Daga karshe ta shi na yi ma na nufi daki rigif haka na fadi saman gado  na fashe da kuka mai gunji ina kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Baba Tabawa hankalinta ya tashi ainun! domin biyo bayana ta yi da abin karin tana cigaba da rarrashina. Ganin halin da nake ciki ya sanya ta ajiye duk abinda yake hannunta ta tararrayoni jikina itama murya na rawa take fad'in." Amina komai ya yi tsanani maganinsa Allah don Allah kada ki karya mini zuciya da wannan kukan na ki, kowane bawa yana tattare da jarabawa, sai dai ta wannan ta fi wannan haka lamarin yake, amma ni a ganina matsalarku karama ce wadda za ku hadu ku maganceta ba tare da kowa ya ji ba, ban san ba ko bayan wadda na sani akwai wata matsalar da take damunki, don Allah ki yi shiru ki yi mini bayani ko Ina da shawarar da zan iya ba ki."
Rungumeta na yi sosai ina kuka na ce." Baba Tabawa na sare zuciyata ta yi rauni ta yi sanyin da ba za ta iya jimirin jure matsaltsalun da ta jure a can baya ba. Ni marainiya yarana ma marayu Baba Tabawa ga damuwa iri

daban-daban wanda nake tare da shi shine mussababbi Baba Tabawa mutumin nan ya tsane ni, wallahi ya hana zuciyata ta huta, bala'in yau daban dana gobe, na gaji! na gaji da auransa ya zame mini karfen kafa a rayuwata."
Ta dinga girgiza kanta tana jimantawa kafin na ji saukar hannunta a kumatuna tana share mini hawaye take ce wa." Ki daina ce wa kin ga ji da ibadar Allah Amina, ba ki sani ba ko wannan itace hanyar shiga aljannarki. Ni kam sai nake ganin kamar kukan dad'i kuke yi, domin kuwa a kaso dari Ubangiji ya yi ba ku kashi tamanin, idan har an samu wani tasgaro da kalubale a cikin kashi darin nan a shawarce godiyar Allah ce za ta biyo baya. Kuna rayuwa ne anan a lullube amma Amina duniyar nan a rikice take wallahi talauci da k'akanakayi ya yi wa al'umma yawa. Matan aure zina zawarawa zina 'yan mata k'ananun yaranmu zina duk domin su ci abinci. A yanzu duk wata mata da Allah ya rufa mata asiri ta samu miji mai kula da iyali da d'aukar nauyin ci da sha da kula da lafiya, to wallahi tallahi ta yi hakuri ta zauna domin idan ta fito rayuwar da za ta fuskanta bayan auran gagarima ce. Amina mace yanzu ko tana da kudi tana kasuwanci muddin ba ta da miji abin zargi ce a wurin mutane koda kuwa tsarkakkiya ce, yanzu nan za ki ji wasu daga cikin marasa fahimta marasa hankali suna kiranta da sunan karuwa. Wannan rayuwar kin yi ta a baya Amina a lokacin duniya ta dan kwance gari bai lalace irin haka ba. Ki yi hakuri ki jure kalubalen gidan auranki in sha Allahu watarana sai labari......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: *Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan. Normal What'sapp group kuma #700 telegram hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*

*TALLAH!*
Follow this link to join my WhatsApp group: https://chat.whatsapp.com/BieW3hHvRNIJLFNloG2CDl

Momyn Hajara GHT supplements

Muna da kayan gyara jiki na maza da mata munada magungunan matsalolin ma'aurata munada magungunan kowacce irin matsala in sha Allah

Hadin Amare
Hadin Ango
Hadin jego

Hadin uwar gida
Hadin babbar mace
Hadin maida tsohuwa yarinya

Muna da Maganin sanyi kowanne iri
Muna da maganin ulcer
Muna da maganin Asthma
Muna da maganin ciwon zuciya
Muna da maganin ciwon Hanta
Muna da Maganin hawan jini
Muna da Maganin ciwon Ido
Muna da Maganin rashin haihuwa
Muna da Maganin skeler
Muna da Maganin kowacce irin cuta da yardar Allah

Sannan kowa zai iyayin register da campanynmu maitarin albarka kasari kaya kasiyar kaci riba sannan Kuma campany yadunga biyanka albashi Duk watan da kayi aiki
Saida kaya shine aikin da zakayi campany ya biya
07012621175
Register 8000 ne kachal
*97*
Sosai maganganun Baba Tabawa suka sanyayyar mini da jiki. Duk abinda ta fad'a babu k'arya. Tabbas na yi gwagwarmayar rayuwa na san komai. Amma ni a irin fargabar da nake ci a yanzu sai nake ganin gwara mini zaman babu laluran miji hankalina zai fi kwanciya shin mai ake nema a cikin aure ne haihuwa to na samu. Ina da dukiyar da zan iya ri'ke kaina da yarana marayu. Allah da kansa ya ce a rabu idan abin ya ci tura, ai gabad'aya lamarin aure da maslaha ya zo domin kuwa abu ne na mutum biyu tare da yarjejeniya kafin tabbatuwarsa.
Fuskata na goge a lokacin na ji idanuwana sun tasa sosai, ba komai ne dalili ba sai irin kukan da na yi wanda na shafe tsayin shekaru rabona da yin irinsa.
Wayata dake saman madubi ta fara kara alamun shigowar kira. Da kanta da sauri ta tafi ta je ta d'auko mini ta ba ni na kar'ba ina dubawa A kunnena kawai na sa wayar kafin na bud'e baki da kyar cikin alamun cushewar murya da dashewa na ce." Na'am.''
Muryarsa babu amo ya furta." Baban Saude ya sauka tun d'azu yanzu haka muna tare da shi sashena da nake saukar ba ki."
Shiru na yi ban ce masa komai ba. Na ji yana fad'in." Ko ba kya ji ne?"
A takaice na ce." Ina ji ya za a yi yanzu to?"
"Ke muke jira?"
Ban bashi amsa ba na kashe wayata jin yadda zuciyata take wani irin harbawa, ina ganin sai mutumin nan ya kaini kasa tukkuna hankalinsa zai kwanta.

Baba Tabawa ta kwashe kayan karin kummalon tana fad'in." Sai dai a had'o miki wani don wannan ya yi sanyi.
Cike da sarkewar murya da numfashi na ce." Ki bari na dawo tukkuna na yi ba'ko daga Maiduguri d'an uwan Mamana ne ya zo."
A sanyaye ta furta." Amma lafiya dai ko?"
Ne ce." Baba Tabawa akan maganar 'barin cikin da na yi ne, shine ya kira shi ya gaya masa don yana zargin zubarwa na yi da gangan.
Sai ta shiga girgiza kanta gabad'aya yanayinta ya nuna alamun damuwa da fargaba ta ce." Haka kawai kuma sai ki zubar da ciki Amina, ai kuna da ilimin addini daidai gwargwado wad'anda ma suke yin sakarcinsu a waje su samu ciki ba su zubar ba sai na sunnah, amma ban ji dadin wannan zargin ba.

Ban ce mata komai ba domin duk bayanin da zan yi mata akan mutumin nan ba zata gane ba. Idan na ce mata shekarun baya na ta'ba yun'kurin zubarwa za ta fara wasu tunanuka marasa kyau akaina kuma bai zama lallai ta fahimci nufina ba tunda ita ai mutuniyar da ce. Akwai tauhidi tare da k'adaita Allah. Shi kam ai ko zan kwana ina rantsuwa ce wa zubewa ya yi babu wata hujja da rantsuwar da zan yi masa ya yarda kan cewa ba hada ba ki muka yi da Hauwa ba.
Hijab na zura a jikina mai fuska har kasa muka fito tare da ita tana ta jadadda maganar har zuwa lokacin Hauwa ba ta fito ba..
Kai tsaye hanyar fita na nufa ita kuma ta nufi kicin babu karsashi da kuzari a tare da ita.

Wuri ne k'ebantace ya ware a gidan domin ganawa da manyan bakinsa na mussaman. Gabad'aya wajen ya fi ko'ina kyau da tsaruwa a gidan. Masu hidima da aikin wajan su kansu na daban ne. Yadda ya sau'ki Baban Saude a sashen ya tabbatar mini da ce wa bai ajiye shi a nesa ba, suna tare domin tun bayan sulhunmu na farko na fara fahimtar abota mai karfi ta shiga tsakaninsu.
Ina dosa kofar da zan shiga falon escort dinshi Sukajiru da Emanuel 'Dahuru sune dai amintattun nasa da basa rabo dashi mussaman ma Sukairaju da duk inda zai tafi tare suke tafiya, bayan wasu jami'ai guda uku da naga ba sa rabo da shi.
ina isa suka fara gaisheni na amsa sama-sama kafin da sauri Sukairaju ya bud'e mini k'ofar na shiga a nutse.
Suna zaune a kujera d'aya hira suke yi cikin faraa da barkwanci tsakiyarsu Loptop ce ta maigidan da alama akwai abinda yake nuna masa a ciki. Center tablet din da yake tsakiyarsu kuwa sha'ke yake da manyan kuloli akwai tazara sosai tsakanina da inda suke tunda girman falon ya shahara sosai. Kafin na kàrasa gabad'aya gwiwata ta sage saboda ban san irin tozarcin da Baban Saude zai yi mini a gaban mutumin nan ba

Cikin nutsuwa na isa wajan da suke zaune na d'an rangwafa kusa dashi kafin na bude baki a nutse na ce." Baban Saude sannu da hanya, fatan duk mutan gidan suna nan lafiya ya su Dada da sauran 'yan uwa."

Ya fuskanceni sosai yana dubana da wani irin yanayin da na kasa tantance shi. Ya ce." Kowa lafiya lau Amina, Dada tana gaisheki ai dana gaya mata cewa zan zo nan wurinki har ta sanya mini rigima wai sai ta biyo ni da k'yar na zame na gudo ba ta sani ba.
Murmushi na yi wanda babu nisha'di ko na miskala zarratin cikin dusheshiyar muryarta da ta ga ji da kuka na ce." Dada kenan ai ba ta ta'ba zuwa ta ga inda nake zaune ba."
Ya sake fuskantata sosai yana fad'in." Tabbas hakane amma ai tana samun labarai a kanki masu dad'i da akasin haka."
Shiru na yi tare da yin kasa da kaina gefe guda Ina ta nazarin manyan mazuban abinci masu daukawar hankali dake jere a saman center tablet din da yake daf da su.
Cikin zuciya na dinga tunanin akan haka. Akwai masu yi masa hidima nau'i daban-daban domin sai na ce duk tsayin zama da shi wasu daga cikin yaransa ma ban san su sosai ba. Amma dai zuciyata ta fi aminta da cewa wannan aikin ba na kowa ba ne face na matarsa da ya rataya fulawar so da k'auna irin ta indiyawa. Momi ce ta yi masa wannan hidimar domin fitar da shi kunya. Ko kad'an hakan bai burge ni ba duk da cewa ta yi ne bisa bin umarinsa amma sai nake zargin babu abinda bai gaya mata ba na abinda ya shafi tsakaninmu da shi. Na sake jin wani irin nauyi da kunci a cikin raina, gabad'aya sabgar mutumin nan ta fice mini daga rai domin kuwa kansa kadai ya sani bai da adalci ko kad'an.

"Ina ita abokiyar zaman naki ai tare nake so na zauna da ku domin tattauna masla'ar da ta kawo gidanki Amina."
Wannan maganar ita ta datse tunanin da na lula na daga kaina cikin kasala da zullumi amma abin da ya ba ni mamaki bai wuce ganin idanuwan maigidan a kaina ba gabad'aya ma hankalinshi na kan 'kafafuna. Har cikin raina kallon ya ta'ba ni domin irin na mutukar 'kurrula ne, nan da nan na fahimci abinda ya assasa hakan bai wuce lallen da ya fito ya zanu radau a kafafuna ba. Da sauri na gyara zaman da na yi na mayar dashi zaman rakuma kafafun suka koma can baya ganin haka ya sanya shi da sauri ya janye idonsa tunda ya fahimci na gan shi sai ya cigaba da duba Loptop din dake gabansa bai ce mana komai ba yana jin Baban Saude yana tambaya Hauwa na kasa ba shi amsa domin kuwa ba na so ko da wasa sunanta ya fito a cikin sha'anina. Hauwa ba ta da wani lefi magani ta ba ni a amtsayinta na ma'aikaciyar lafiya bai yiwuwa saboda yana jin haushinta ya jingina mata lefin da ba ta da hurumi a ciki.

Ya sake maimaita tambayarsa. Sai kawai na rushe da kuka mai tafe da gunji na ce." Baban Saude ita Hauwa ina ruwanta, tsautsayi ne kawai ya faru a matsayinta na ma'aikaciyar lafiya ta bada gudummuwarta amma a ganina bata da lefi a cikin wannan maganar.
Shiru ya yi kawai yana kallona cike da mamakin ganin irin kukan da nake sharba kuma mai tafe da jan majina da shashsheka. Yanayinsa ya d'an nuna sanyi da sasaauci, ganin haka ya sanya na cigaba da rerawa da babban sauti

Ina yi ina jan hanci. Wajan in banda sautin kukana babu abinda yake tashi. Baban Saude kawai ya zuba mini ido, shi kuma wanda ya assasa zaman kansa yana dukufe a computr kanzil bai ce mana ba.

Littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba sister.

Ya d'an sauke ajiyar zuciya cikin kulawa da da tausayi irin na iyaye a cikin idonsa ya ce. "Amina
ashe kenan ba ni da hurumi ko ban kai abokiyar zamanki ta taso ta gaishe ni ba kenan Amina, ai ni tambayarki ita kawai na yi na ce da ke ina take ai ita din ma 'yata ce kamar ke din ko ba haka ba ne."
Na gyada kaina tare da sanya hannu na ja hanci cikin reshin kuka na ce." To Baban Saude ai ban san me ya gaya maka  game da mu ba. Shine dalilin da ya sanya ka ji na ce haka, idan har ba zai iya yadda da kaddara da abinda Allah Ya shiryo ba ai bai kamata ya na hada ni dak.....Ban kàrasa ba ya buga hannun kujerar da yake zauna ya furta." Me ki ka ji na ce miki Amina, wato a gabana din ma kaifin harshe za ki yi, idan shi kin raina shi saboda kuna kwanciya a shimfida da d'aya ai ni ya wuce a ce ki yi mini jayayya bisa umarnina, shin wai ko kin manta wanene a gabanki ne, kuma ai ba mu zauna an ji ta bakin kowa ba tukkuna kada ki 'bata mini rai Amina."
Shiru na yi gabana na bugawa da karfi da karfi, don sasasucin dana hanga a fuskarsa ya 'bace bat ya dawo asalin baban Saude mafada ci.
"Idan na isa ki tashi ki je ki kira wo mini ita."
Ya fad'a cikin sigar bada umarni.
Ban ce komai ba na tashi na kama hanyar fita k'afafuna kamar an doke mini da ta'barya. Allah Ya yi wa Baban Saude wani irin kwarjina da haiba  da wata baiwa wadda idan ya yi magana ko babu fad'a a ciki sai mutum ya nutsu. Yanayinsu daya da jarumin film din nan na Hausa (Tahir fagge)
Ina shiga d'akin na sameta ta yi wanka tana cin indomin da Baba ta dafa mata
Ganin yadda na shigo ya sanya ta tsira mini ido har na isa wurin da take zaune. Kafin na furta komai ta riga ni ta hanyar fad'in." Lafiya na ga idonki a kumbure ko mutuwa aka yi ne ban sani ba ina ta baccin asara.''
Na girgiza kaina tare da fad'in." Babu wanda ya mutu Hauwa mijinki ne ya kai 'kararmu wurin Baban Saude."
Ta yi shiru tana maimata sunan baban Saude kafin ta furta." Oh Yayan Mamanku na maiduri ko?"
Na ce." Shi fa, bai jima da sauka ba, yana can sashensa na baki ya ce na kira wo ki muje tare.
Karamin tsaki ta ja kafin ta ce." To akan me Amina ba ki gaya masa cewa zaman idda nake yi ba babu igiyar aure a tsakaninmu, akan me kuma zai sanya ni a cikin abinda ya shafe ku."

"Saboda yana zargin mun had'a baki tare mun zubar masa da ciki. Hauwa musabbabi akan 'barin da na yi kwanaki bai yarda zubewa ya yi da tsautsayi ba. Ga ni yake yi zubar da shi na yi ina sane."
Ta dube ni da mamaki kafin ta ce." To shine me, ai ina ganin ni ba ni da hurumi anan Amina, wallahi kwata-kwata ma ni fa ba na jin dad'in jikina don Allah kada ku sanya ni cikin wannan cakwakiyartaku."
Na ce." Na sani Hauwa, ki ta so dai mu je don Allah idan ya so ni zan gayawa Baban Saude ba ki da lefi, kada ki ce ba za ki je ba, wannan zai sake tabbatar musu da cewa babu gaskiya a tare da mu."
Jim ta yi na sakkoni kafin ta ce."shikkenan mu je to." Ta ajiye plate din indomin wanda dama saura karashe kad'an ta d'auki ruwa ta kurba sannan ta tashi ina tsaye ina kallonta ta d'auko hijabin dake ta salla ta zura sannan ta dube ni. Ban furta komai ba na juya da niyyar fita ta rufo mini baya.
A ka ci sa'a kuwa baba Tabawa ba ta fito ba tana d'akinta.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

A LURA DA WANNAN.
Idan har kina da niyyar biyana hakkina kudin karatu kawai za ki biya kada ki ce mini kina son book3 ko book4 ni dai book1 kadai na bayar a matsayin free peges ba ni na hada doc din 2 3 ba. Ga Details dina nan a sama kisa kudin ki yi karatu cikin nutsuwa da kwanciyar hankali Allah Ya tsarkake mana zuk'ata ya hane mu tad'e kafafun junanmu ya hana mu dakushe nasarar junanmu. Allah Ya bawa kowa a hannunsa. Allah Ya taimaka mana neman na kanmu ina kara fad'i wannan littafi na kudi ne  ki biya mai hakki hakkinta kafin ki karantà. Na gode.

*Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
*98*
Yana cin abinci a lokacin da muka shiga. Cima ce iri iri da snakes tabbacin an shirya sune domin shi akwai wad'anda ma bai bud'e ba suna cikin wamars
Wanda dai yake gabansa farfesu kayan cikin rago ne ya yi kyau sosai da katon bread yana dangwala gefe kuma black tea ne babu madara tunda dama tun asali sanin da na yi masa ba ya shan madara da zuma sai idan ya zama dole, amma ko zaman da na yi a gidansa haka yaransa suke sayo mana madara ta gwangwani duk ranar da suka yi shayi kowa da tasa amma shi haka wadda take da girki zata d'auki tsurar fulas dinsa daban da ba'kin shayinsa a ciki ta kai masa dakinsa.
Cike da nutsuwa Hauwa ta gaishe shi ma ya amsa da kulawa. Wurin ya d'auki shiru tun bayan gaisuwar da suka yi. Sai da ya kammala tukkuna a nutse ya goge bakinsa da tissue ya dube mu gabad'aya kafin ya furta." Hauwa da gaske ke ce ki ka tura Masa'udu direbanku ya sayowa Amina maganin wankin mahaifa?"
Ta dube shi a tsanake ta furta." E, ni ce Baban Saude."
Da d'an mamaki a tare da shi ya ce." Kenan da gaske hade baki ku ka yi ba kwa tsoron Allah dama?"
Murmushin takaici ta yi kafin ta furta.'' Ko daya Baban Saude kaddara ce ta gifta wani lamari mai rikitarwa ya faru a gidan nan gabad'aya muka shiga

cikin gigita, to wannan ya assasawa Amina abortion bisa tsautsayi cikinta ya zube . Ganin yadda ya fice ba tare da an samu wata tangarda ba ya sanya na rubuta magani jikin takarda na sanya aka sayo mata domin ya k'ara taimaka mata wurin wanko abinda ya rage a mahaifarta?
Ya ce." A lokacin mai yasa kafin ki yanke hukuncin yin hakan ba ki yi yun'kurin sanar da mijinku ba, ko ko cikin bashi da uba ne?"
Shiru ta yi ta kasa cewa komai sai da ya sake maimaita maganarsa tukkuna ta ce." Wallahi ban san abinda yake tsakaninsu ba domin kuwa na d'auka ita Aminar ta gaya masa shine dalili kuma dai ni kaina ba magana yake yi mini ba a lokacin gaba yake yi da ni."
"Shine dalilin da ya sanya ki kenan yin gaban kanki a matsayinki na ma'aikaciyar lafiya ai kin fi karfin ki yi masa magana dalili yana fushi dake, kamar doka ce babba a kowane asibiti sai da amincewa da sanya hannun mai ruwa da tsaki, ina nufin wanda yake da hurumi akan abu, akan wane dalili zai amince cewa da gaske k'addara ce ba shirya zubarwa kuka yi a tare ba?"
Ta fashe da kuka tana ce wa." To ni dai Allah ne shaidata Baban Saude ni ma cikin ne fa da ni, a ganina kafin na bada goyon bayan wata ta zubar da nata ai ni zan yi yun'kurin zubar da nawa dalilin abinda ya ratsa tsakanina da shi, ai gashinan a zaune yana ji ni ba matarsa ba ce yanzu domin ya sake ni."
Baban Saude ya dube shi da saurin gaske domin maganar Hauwa ta karshe ta kidima shi.
Bai ce komai ba still hankalina na kan computer dake gabansa kuma bai dago ya dubi Baban Sauden ba..
Sai ya juyo gare mu yana fad'in." Ban san da haka ba Hauwa, kuma ni nan ban titsiyeki domin naga iya gudun ruwanki ba. Abinda ya sanya ita Amina muke zarginta da aikatawaa saboda ta ta'ba yun'kurin yin hakan a shekarun baya, abinda ku ka yi ba daidai ba ne, mai yasa a lokacin da za ki aika Masa'udu ya sayu maganin ba ki kira shi kin sanar da shi ba a matsayinsa na jagoranku kuma wanda yake da hakki a kan cikin."
Shiru ta yi ba ta ce komai ba.
Sai ya cigaba da cewa."
ko ni nan babu wata mace da za ta yi mini haka na amince da gaskiyarta. Sannan ya sanar da ni cewa kun had'a kai kun ware d'ayar mutuniyar kirkin cikinku, ai duk macen da mijinta zai zauna ya dinga yabo tare da fad'in kirkinta ita ta amsa sunan mace ba irinku 'yan amshin shata ba, to me ta yi muku, mutuwa ce fa ta raba tsakaninta da mijinta mai rasuwa Alhaji Amadu, kuma ya barwa Amininsa wasiyya akan ya aureta domin cigaba da kula da ita da yaranta. Ban ga matar nan ido da ido ba, amma zaman nan da na yi kaf alheri da kyautatawarta mijinta yake gaya mini, ni ma gashi na ga ni yadda ta sauke ni da hidima daban daban tamkar wani basarake. Ba ku ji kunya ba Hauwa, ita fa macen da ta fi biyayya ga miji itace sarauniyarsa wannan matar ta dame ku ta shanyeku a komai sannan kun yi sake wanda kuke jin haushinta dominsa ya fi sonta kun hade mata kai shi kuma ya had'e kai da ita, ina kara gaya muku kun cika shashasha!"

Tsit! wurin ya dauka bayan yin shirunsa, zuciyata ban da dokawa babu abinda take yi wannan wane irin cin mutunci ne da cin fuska Baban Saude ya shirya yi mini. Menene lefin Hauwa anan da za a sanyata a gaba da cin zarafi haka. Shikkenan a rayuwa mutam ba zai yi kuskure ba.
Wasu hawaye masu d'umi da yaji suka fara simiyowa suna bin kumatuna. Wannan karon hawayen ne kawai suke fita masu zafi da ciwo babu damar yin gunji sai dai ciwon zuciya.
Ya d'auki kofin shayinsa ya kurba kafin ya cigaba da ce wa." Gaskiya ku gyara domin kuwa babu wata gadara da za ku yi a karkashin ikon namiji, mijinku gashi nan yana ji ko shine ya yi ba daidai babu ruwana zan titsiye shi na gaya masa gaskiya ko ta yi masa dadi ko ta yi masa zafi wannan shine zaman tare Alhaji Tajo ba surukina ba ne a yanzu abokina ne, mun yi sha'kuwa ta ban mamaki a sha'aninsa zan yi tsalle na dire a ciki koda kuwa bai shafi Amina ba. kuma za ki koma dakinki Hauwa kin ji ko?"
Tana kuka ta ce." A, a Baban Saude ni kam na ha'kura gaskiya wallahi zuciyata ba za ta iya d'auka ba."
Baban Saude ya yi shiru yana kallonta da mamaki kafin ya ce."Zuciyarki ba za ta iya d'aukar me ba?"
Kafin ta furta wani abu ya rigata ta hanyar fad'in." Ka ji abinda na ke gaya maka ko, gabad'ayansu fa Maryam ta tsone musu idan ba haka ba menene na fad'in wannan maganar, zuciyarta ba za ta iya d'aukar ganin Ina tare da Maryam ba, idan har ina son zama da ita amsar kawai na saki Maryam sai zuciyarta ta d'auka."

Yana ajiye maganarsa na ce. "Baban Saude gabad'aya maganar ba haka take ba zahirin gaskiya bai gaya maka wasu abubuwan da suke faruwa ba. Wanda ya zama lallai ace an zauna a kansu. Wallahi ba mu ware Hajiya Maryam ba illa iyaka shi da ya fifita a kanmu, gashi nan a zaune idan har na yi masa sharri to ni Amina ina ro'kon Allah Ya d'auki raina a yanzu wallahi tallahi zalitarmu yake yi." Na kai karshen maganar muryarta na rawa.
Ya nisa kafin ya ce." Ai dama shari'a ta aure ba za a ce mutum d'aya ne yake da laifi dole ta kowanne b'angare a samu abin fad'a, kuma dama ni ba ni da niyyar rufe wannan mas'alar ba tare dana tambayi kowaccenku ba,
ni babban abinda ya ba ni haushi daku shine yadda kuka had'ewa abokiyar zamanku kai kuka ware ta sannan da ki ka san cikin ya zube mai yasa ba ki gaya masa ba har sai da aka ja lokaci dole ya d'ora alamar tambaya a kanku."
Hauwa tana kuka ta ce." Dukan mu fa yake yi akan ita Hajiya Maryam din a gaban mai'aikinmu Baba Tabawa ko ita sheda ce ya dinga marina ya tunkud'e ni da karfi na fadi har sai da na yi targad'e a hannuna duk da hakan bai ishe shi ya sake ni."
Ta dinga kuka da iyakacin karfinta! Baban Saude jikinsa ya yi sanyi ya dinga maimaita kalmar duka yana kallonsa shi kuma jikinsa duk ya mutu don da alama bai tsammaci faruwar hakan ba.
Baban Saude ya dube ni yana fad'in." Kenan kema sheda ce Amina?"

Na gyada kaina tare da fad'in." I, wallahi ni na shiga tsakaninsu ma." Na fad'a a dan tsorace dalili ina jin tsoron allura ta tono garma ya gaya masa na ta'ba toshe masa hanci da fillo.
Ya ce."To akan me, Allah ya taimakeka dama akwai duka mai illatarwa a cikin shara'din aure kuma mace mai d'auke da yaron ciki, anya akwai imani a nan?"
Fuskarsa ta had'e sosai yana kallonsa da mamaki.
Sai ya kasa daga kansa ya dube shi cikin kame-kame ya ce." Baban Saude yaran nan ba su da kirki ko kad'an ni kuma ban yi mata dukan da zai illatata ba."
Cikin 'yar 'kure baban Saude ya ce." To wane iri ka yi mata?"
Ya furta." Marinta na yi?"
Ya ce." To ai mari karshen tozarci kenan a mari mutum a fuska yanzu tsakani da Allah ko tunkiya ka daure a gidanka ka mare ta, ina lefin ma gabar da kake yi da su duk da itama a shari'a haramun ce, anya kuwa ranka shi dad'e ka shirya sulhunta gidanka kuwa?"
Shiru ya yi bai ce masa komai ba.
Sai ya juyo kaina yana fad'in." Sai me kuma?"
Na ce." Magana ce akan yaranmu da ya kwashe ya kai wa matar tasa, to wannan ma yana daya daga cikin abinda yake mana ciwo koyaushe idan mun yi magana sai ya nuna kamar ya fi mu iko a kansu yana kiranmu da marasa tarbiya komai muka yi ba mu iya ba."
Ya dinga jijjiga kansa kafin ya sake dubansa a karo na kusan hud'u kansa yana kasa bai dago ba tsabar kunya ta hana shi musantawa yadda na lura yana tsoron ya tanka mu sake 'baro wata wata maganar da za ta zama abar tattaunawa tare da nuna masa kuskuransa.
Baban Saude ya ce." Idan kuwa hakane ka takewa yaran nan hakkinsu Alhaji Tajo kasan tsananin so da k'auna da sha'kuwar dake tsakanin uwa da d'anta kuwa? me yasa ka d'auki ga'barar raba sha'kuwa iyaye da 'ya'yansu. Mai yasa ka fifita Maryam a kan su? Idan har gaskiya ne abinda suka fad'a tabbas akwai zama tsakani na dakai na mussaman ko ba mu yi yanzu ba za mu anan gaba wannan ba daidai ba ne bari na gaya maka, ai ka haihu to muddin kana so 'ya'yanka mata su rayu cikin mutunci da kulawa a gidan mazajensu to kada ka zalinci 'ya'yan wasu tare da biyewa son zuciya. Maganar nan fa gaskiya ce da ake cewa duk abinda ka yi sai an yi maka." Ya nisa kafin ya cigaba da cewa."
Ban yadda ba gaskiya dole nasan a cikinsu akwai wadda ta fi kyautata maka kamar yadda ka gaya mini yanzu kana jin dadin zama da Maryam. Amma baka da dalili mai karfi ko a shari'a da za ka kwashe musu yaransu ka bawa wata bayan duk suna raye da ransu da lafiyarsu ba su mutu ba. Ina lefin ma su dinga zuwa suna gaisheta suna dawowa gaban iyayensu."
Ya yi shiru dai bai ce komai ba. Yana ta d'an lallatsa computer amma na tabbata babu abinda yake fuskanta. Jikinsa kuma ya yi sanyi ainun.

Ganin haka ya sanya Baban Saude ya dube ni a tsanake ya ce." Ku yi hakuri ni bai gaya mini hakan ba, kuma in sha Allahu zan baku gudumuwa. Ke Hauwa za ki koma dakinki in sha Allahu rabbi."

Ganin mun yi shiru ya sanya ya sake sassautawa tare da furta "kuyi hakuri kun ji salihan mata ba a san su da irin wannan sakarcin ba, suna d'aukar kishiyarsu 'yar uwarsu kamar yadda ku ka d'auki lamarin junanku da muhimmanci to itama ku d'auketa hakan ku daina ware ta, ku yi mu'amula da ita tsakanina da Allah, idan ma tana cutarku a boye sai Allah Ya saka muku lefinta daya yaranku da suke hannunta to ku d'auki alhakin hakan ku dora shi akan mijinku domin da bai kai mata su ba ai ba zata zo gabanku ta kwashe muku yara ba. Kada ku munana zato a kanta ko kuma ku 'kyamace ta, ku zauna ku yi tunani sosai ku gano akan me yasa maigidanku ya fi shau'kinta domin tunda na zauna anan yake ta yabonta har sai da na ji wani iri a raina mai yasa ba za ku yi koyi da ita ba?"
Shiru muka yi gabad'ayanmu. Sai ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Ni ban zo gidanku domin na sanya ku koke-koke ba, ita Amina ta san wanene ni, ta kuma san halina ciki da waje babu yadda za a yi na goyi da bayan karya na take gaskiya ba na so a sake gaya mini kun aikata wani shashancin makamancin wannan, ku dinga sanar da maigidanku matsala idan ta taso tunda ai ba zaman kan ku kuke yi ba ko?"
Babu wanda ta ba shi amsa. Ya cigaba da cewa." Na gode da nutsuwar da ku ka yi kuka saurare ni, ina fatan a ce kada na zama dattijon banza a idonku bayan na gusa ku cigaba daga inda ku ka tsaya, Amina hakan ba za ta yi muku kyau ba."
Jin ya ambaci sunana na ce." In sha Allahu rabbi hakan na za ta sake faruwa ba."
Ya dube Hauwa yana fad'in." Amina ta baki lambar wayata duk ranar da ya sake dukanki sai ki kira ni ki sanar da ni."
Ta ce." To shikkenan Baban Saude na gode....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma

Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

A LURA DA WANNAN.
Idan har kina da niyyar biyana hakkina kudin karatu kawai za ki biya kada ki ce mini kina son book3 ko book4 ni dai book1 kadai na bayar a matsayin free peges ba ni na hada doc din 2 3 ba. Ga Details dina nan a sama kisa kudin ki yi karatu cikin nutsuwa da kwanciyar hankali Allah Ya tsarkake mana zuk'ata ya hane mu tad'e kafafun junanmu ya hana mu dakushe nasarar junanmu. Allah Ya bawa kowa a hannunsa. Allah Ya taimaka mana neman na kanmu ina kara fad'i wannan littafi na kudi ne  ki biya mai hakki hakkinta kafin ki karantà. Na gode.

*Wannan littafin na kudi ne vip 1k akan telegram. Normal What'sapp group kuma #700 hanyar da za a biya kudin ita ce wannan...0542382124...Binta Umar gtbank ko kuma 7084653262...Binta Umar Opey bank. 'Yan nijar dala dari katin airtel za ku tura mini  bayan kun kankare hoton. A tura da sheda ta wannan lambobin iya What'sapp kawai.*
*07084653262*
*08089965176*
*V-VIP AREWA PEN*
 *98*
Yana cin abinci a lokacin da muka shiga. Cima ce iri iri da snakes tabbacin an shirya sune domin shi akwai wad'anda ma bai bud'e ba suna cikin wamars
Wanda dai yake gabansa farfesu kayan cikin rago ne ya yi kyau sosai da katon bread yana dangwala gefe kuma black tea ne babu madara tunda dama tun asali sanin da na yi masa ba ya shan madara da zuma sai idan ya

zama dole, amma ko zaman da na yi a gidansa haka yaransa suke sayo mana madara ta gwangwani duk ranar da suka yi shayi kowa da tasa amma shi haka wadda take da girki zata d'auki tsurar fulas dinsa daban da ba'kin shayinsa a ciki ta kai masa dakinsa.
Cike da nutsuwa Hauwa ta gaishe shi ma ya amsa da kulawa. Wurin ya d'auki shiru tun bayan gaisuwar da suka yi. Sai da ya kammala tukkuna a nutse ya goge bakinsa da tissue ya dube mu gabad'aya kafin ya furta." Hauwa da gaske ke ce ki ka tura Masa'udu direbanku ya sayowa Amina maganin wankin mahaifa?"
Ta dube shi a tsanake ta furta." E, ni ce Baban Saude."
Da d'an mamaki a tare da shi ya ce." Kenan da gaske hade baki ku ka yi ba kwa tsoron Allah dama?"
Murmushin takaici ta yi kafin ta furta.'' Ko daya Baban Saude kaddara ce ta gifta wani lamari mai rikitarwa ya faru a gidan nan gabad'aya muka shiga cikin gigita, to wannan ya assasawa Amina abortion bisa tsautsayi cikinta ya zube . Ganin yadda ya fice ba tare da an samu wata tangarda ba ya sanya na rubuta magani jikin takarda na sanya aka sayo mata domin ya k'ara taimaka mata wurin wanko abinda ya rage a mahaifarta?
Ya ce." A lokacin mai yasa kafin ki yanke hukuncin yin hakan ba ki yi yun'kurin sanar da mijinku ba, ko ko cikin bashi da uba ne?"
Shiru ta yi ta kasa cewa komai sai da ya sake maimaita maganarsa tukkuna ta ce." Wallahi ban san abinda yake tsakaninsu ba domin kuwa na d'auka ita Aminar ta gaya masa shine dalili kuma dai ni kaina ba magana yake yi mini ba a lokacin gaba yake yi da ni."
"Shine dalilin da ya sanya ki kenan yin gaban kanki a matsayinki na ma'aikaciyar lafiya ai kin fi karfin ki yi masa magana dalili yana fushi dake, kamar doka ce babba a kowane asibiti sai da amincewa da sanya hannun mai ruwa da tsaki, ina nufin wanda yake da hurumi akan abu, akan wane dalili zai amince cewa da gaske k'addara ce ba shirya zubarwa kuka yi a tare ba?"
Ta fashe da kuka tana ce wa." To ni dai Allah ne shaidata Baban Saude ni ma cikin ne fa da ni, a ganina kafin na bada goyon bayan wata ta zubar da nata ai ni zan yi yun'kurin zubar da nawa dalilin abinda ya ratsa tsakanina da shi, ai gashinan a zaune yana ji ni ba matarsa ba ce yanzu domin ya sake ni."
Baban Saude ya dube shi da saurin gaske domin maganar Hauwa ta karshe ta kidima shi.
Bai ce komai ba still hankalina na kan computer dake gabansa kuma bai dago ya dubi Baban Sauden ba..
Sai ya juyo gare mu yana fad'in." Ban san da haka ba Hauwa, kuma ni nan ban titsiyeki domin naga iya gudun ruwanki ba. Abinda ya sanya ita Amina muke zarginta da aikatawaa saboda ta ta'ba yun'kurin yin hakan a shekarun baya, abinda ku ka yi ba daidai ba ne, mai yasa a lokacin da za ki aika Masa'udu ya sayu maganin ba ki kira shi kin sanar da shi ba a matsayinsa na jagoranku kuma wanda yake da hakki a kan cikin."
Shiru ta yi ba ta ce komai ba.
Sai ya cigaba da cewa."

ko ni nan babu wata mace da za ta yi mini haka na amince da gaskiyarta. Sannan ya sanar da ni cewa kun had'a kai kun ware d'ayar mutuniyar kirkin cikinku, ai duk macen da mijinta zai zauna ya dinga yabo tare da fad'in kirkinta ita ta amsa sunan mace ba irinku 'yan amshin shata ba, to me ta yi muku, mutuwa ce fa ta raba tsakaninta da mijinta mai rasuwa Alhaji Amadu, kuma ya barwa Amininsa wasiyya akan ya aureta domin cigaba da kula da ita da yaranta. Ban ga matar nan ido da ido ba, amma zaman nan da na yi kaf alheri da kyautatawarta mijinta yake gaya mini, ni ma gashi na ga ni yadda ta sauke ni da hidima daban daban tamkar wani basarake. Ba ku ji kunya ba Hauwa, ita fa macen da ta fi biyayya ga miji itace sarauniyarsa wannan matar ta dame ku ta shanyeku a komai sannan kun yi sake  wanda kuke jin haushinta dominsa ya fi sonta kun hade mata kai shi kuma ya had'e kai da ita, ina kara gaya muku kun cika shashasha!"
Tsit! wurin ya dauka bayan yin shirunsa, zuciyata ban da dokawa babu abinda take yi wannan wane irin cin mutunci ne da cin fuska Baban Saude ya shirya yi mini. Menene lefin Hauwa anan da za a sanyata a gaba da cin zarafi haka. Shikkenan a rayuwa mutam ba zai yi kuskure ba.
Wasu hawaye masu d'umi da yaji suka fara simiyowa suna bin kumatuna. Wannan karon hawayen ne kawai suke fita masu zafi da ciwo babu damar yin gunji sai dai ciwon zuciya.
Ya d'auki kofin shayinsa ya kurba kafin ya cigaba da ce wa." Gaskiya ku gyara domin kuwa babu wata gadara da za ku yi a karkashin ikon namiji, mijinku gashi nan yana ji ko shine ya yi ba daidai babu ruwana zan titsiye shi na gaya masa gaskiya ko ta yi masa dadi ko ta yi masa zafi wannan shine zaman tare Alhaji Tajo ba surukina ba ne a yanzu abokina ne, mun yi sha'kuwa ta ban mamaki a sha'aninsa zan yi tsalle na dire a ciki koda kuwa bai shafi Amina ba. kuma za ki koma dakinki Hauwa kin ji ko?"
Tana kuka ta ce." A, a Baban Saude ni kam na ha'kura gaskiya wallahi zuciyata ba za ta iya d'auka ba."
Baban Saude ya yi shiru yana kallonta da mamaki kafin ya ce."Zuciyarki ba za ta iya d'aukar me ba?"
Kafin ta furta wani abu ya rigata ta hanyar fad'in." Ka ji abinda na ke gaya maka ko, gabad'ayansu fa Maryam ta tsone musu idan ba haka ba menene na fad'in wannan maganar, zuciyarta ba za ta iya d'aukar ganin Ina tare da Maryam ba, idan har ina son zama da ita amsar kawai na saki Maryam sai zuciyarta ta d'auka."

Yana ajiye maganarsa na ce. "Baban Saude gabad'aya maganar ba haka take ba zahirin gaskiya bai gaya maka wasu abubuwan da suke faruwa ba. Wanda ya zama lallai ace an zauna a kansu. Wallahi ba mu ware Hajiya Maryam ba illa iyaka shi da ya fifita a kanmu, gashi nan a zaune idan har na yi masa sharri to ni Amina ina ro'kon Allah Ya d'auki raina a yanzu wallahi tallahi zalitarmu yake yi." Na kai karshen maganar muryarta na rawa.
Ya nisa kafin ya ce." Ai dama shari'a ta aure ba za a ce mutum d'aya ne yake da laifi dole ta kowanne b'angare a samu abin fad'a, kuma dama ni ba ni da niyyar rufe wannan mas'alar ba tare dana tambayi kowaccenku ba,

ni babban abinda ya ba ni haushi daku shine yadda kuka had'ewa abokiyar zamanku kai kuka ware ta sannan da ki ka san cikin ya zube mai yasa ba ki gaya masa ba har sai da aka ja lokaci dole ya d'ora alamar tambaya a kanku."
Hauwa tana kuka ta ce." Dukan mu fa yake yi akan ita Hajiya Maryam din a gaban mai'aikinmu Baba Tabawa ko ita sheda ce ya dinga marina ya tunkud'e ni da karfi na fadi har sai da na yi targad'e a  hannuna duk da hakan bai ishe shi ya sake ni."
Ta dinga kuka da iyakacin karfinta! Baban Saude jikinsa ya yi sanyi ya dinga maimaita kalmar duka yana kallonsa shi kuma jikinsa duk ya mutu don da alama bai tsammaci faruwar hakan ba.
Baban Saude ya dube ni yana fad'in." Kenan kema sheda ce Amina?"
Na gyada kaina tare da fad'in." I, wallahi ni na shiga tsakaninsu ma." Na fad'a a dan tsorace dalili ina jin tsoron allura ta tono garma ya gaya masa na ta'ba toshe masa hanci da fillo.
Ya ce."To akan me, Allah ya taimakeka dama akwai duka mai illatarwa a cikin shara'din aure kuma mace mai d'auke da yaron ciki, anya akwai imani a nan?"
Fuskarsa ta had'e sosai yana kallonsa da mamaki.
Sai ya kasa daga kansa ya dube shi cikin kame-kame ya ce." Baban Saude yaran nan ba su da kirki ko kad'an ni kuma ban yi mata dukan da zai illatata ba."
Cikin 'yar 'kure baban Saude ya ce." To wane iri ka yi mata?"
Ya furta." Marinta na yi?"
Ya ce." To ai mari  karshen tozarci kenan a mari mutum a fuska yanzu tsakani da Allah ko tunkiya ka daure a gidanka ka mare ta, ina lefin ma gabar da kake yi da su duk da itama a shari'a haramun ce, anya kuwa ranka shi dad'e ka shirya sulhunta gidanka kuwa?"
Shiru ya yi bai ce masa komai ba.
Sai ya juyo kaina yana fad'in."  Sai me kuma?"
Na ce." Magana ce akan yaranmu da ya kwashe ya kai wa matar tasa, to wannan ma yana daya daga cikin abinda yake mana ciwo koyaushe idan mun yi magana sai ya nuna kamar ya fi mu iko a kansu yana kiranmu da marasa tarbiya komai muka yi ba mu iya ba."
Ya dinga jijjiga kansa kafin ya sake dubansa a karo na kusan hud'u kansa yana kasa bai dago ba tsabar kunya ta hana shi musantawa yadda na lura yana tsoron ya tanka mu sake 'baro wata wata maganar da za ta zama abar tattaunawa tare da nuna masa kuskuransa.
Baban Saude ya ce." Idan kuwa hakane ka takewa yaran nan hakkinsu Alhaji Tajo kasan tsananin so da k'auna da sha'kuwar dake tsakanin uwa da d'anta kuwa? me yasa ka d'auki ga'barar raba sha'kuwa iyaye da 'ya'yansu. Mai yasa ka fifita Maryam a kan su? Idan har gaskiya ne abinda suka fad'a tabbas akwai zama tsakani na dakai na mussaman ko ba mu yi yanzu ba za mu anan gaba wannan ba daidai ba ne bari na gaya maka, ai ka haihu to muddin kana so  'ya'yanka mata su rayu cikin mutunci da kulawa a gidan mazajensu to kada ka zalinci 'ya'yan wasu tare da biyewa son zuciya. Maganar nan fa

gaskiya ce da ake cewa duk abinda ka yi sai an yi maka."  Ya nisa kafin ya cigaba da cewa."
 Ban yadda ba gaskiya dole nasan a cikinsu akwai wadda ta fi kyautata maka kamar yadda ka gaya mini yanzu kana jin dadin zama da Maryam. Amma baka da dalili mai karfi ko a shari'a da za ka kwashe musu yaransu ka bawa wata bayan duk suna raye da ransu da lafiyarsu ba su mutu ba. Ina lefin ma su dinga zuwa suna gaisheta suna dawowa  gaban iyayensu."
Ya yi shiru dai bai ce komai ba. Yana ta d'an lallatsa computer amma na tabbata babu abinda yake fuskanta. Jikinsa kuma ya yi sanyi ainun.

Ganin haka ya sanya Baban Saude ya dube ni a tsanake ya ce." Ku yi hakuri ni bai gaya mini hakan ba, kuma in sha Allahu zan baku gudumuwa. Ke Hauwa za ki koma dakinki in sha Allahu rabbi."

Ganin mun yi shiru ya sanya ya sake sassautawa tare da  furta "kuyi hakuri kun ji salihan mata ba a san su da irin wannan sakarcin ba, suna d'aukar kishiyarsu 'yar uwarsu kamar yadda ku ka d'auki lamarin junanku da muhimmanci to itama ku d'auketa hakan ku daina ware ta, ku yi mu'amula da ita tsakanina da Allah, idan ma tana cutarku a boye sai Allah Ya saka muku lefinta daya yaranku da suke hannunta to ku d'auki alhakin hakan ku dora shi akan mijinku domin da bai kai mata su ba ai ba zata zo gabanku ta kwashe muku yara ba. Kada ku munana zato a kanta ko kuma ku 'kyamace ta, ku zauna ku yi tunani sosai ku gano akan me yasa maigidanku ya fi shau'kinta domin tunda na zauna anan yake ta yabonta har sai da na ji wani iri a raina mai yasa ba za ku yi koyi da ita ba?"
Shiru muka yi gabad'ayanmu. Sai ya nisa kafin ya cigaba da ce wa." Ni ban zo gidanku domin na sanya ku koke-koke ba, ita Amina ta san wanene ni, ta kuma san halina ciki da waje babu yadda za a yi na goyi da bayan karya na take gaskiya ba na so a sake gaya mini kun aikata wani shashancin makamancin wannan, ku dinga sanar da maigidanku matsala idan ta taso tunda ai ba zaman kan ku kuke yi ba ko?"
Babu wanda ta ba shi amsa. Ya cigaba da cewa." Na gode da nutsuwar da ku ka yi kuka saurare ni, ina fatan a ce kada na zama dattijon banza a idonku bayan na gusa ku cigaba daga inda ku ka tsaya, Amina hakan ba za ta yi muku kyau ba."
Jin ya ambaci sunana na ce." In sha Allahu rabbi hakan na za ta sake faruwa ba."
Ya dube Hauwa yana fad'in." Amina ta baki lambar wayata duk ranar da ya sake dukanki sai ki kira ni ki sanar da ni."
Ta ce." To shikkenan  Baban Saude na gode....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/3, 8:38 PM] matar mijinta: □□□☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*

*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Paid book 1k akan telegram via 0542382124.. Binta Umar gtbank. Ko 07084653262*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*99*
Cike da kulawa ya ce." Ni ma na gode Hauwa, kun tar'be hannu biyu kuma kun karrama ni, Allah Ya yi muku albarka bakidaya."
Muka amsa da "Amin a tare."

Maigidan ya rufe Loptop din gabansa yana fad'in." Ba za dai ka bari ka bi jirgin yamma ba kenan."
Ya ce." Motar ma za ta kai ni gida cikin k'oshin lafiya, abinda na saba da zamanta tunda ni ba mazauni ba ne. "

Ya gyada kansa kafin ya furta.'' To babu damuwa idan mun tashi sai mu shiga can wajan Maryam din ku gaisa ko."
Baban Saude ya furta." Ai ya zame mini dole ranka shi dad'e wannan alatun da aka shirya mini yana da kyau na je yin godiya."
Ya kuwa fashe da dariya yana d'an dukan kafad'arsa."
Takaicin abinda suke yi ya dinga nukurkusata don sai nake ganin kamar ma da gayya suke  yin hakan. Abin mamaki da al'ajabi wai yau Baban Saude ne da mijina suke wasa da barkwanci irin na abokai. Na girgiza kaina a yayin da nake jin wani irin bala'in takaici na taso mini ban ankara ba na ji motsin Hauwa ta mike tsaye kafin ta d'an rankwafa tana fad'in." Baban Saude a sauka lafiya don Allah a gaishe da mutan nan gidan da kyau."
Da sauri ya dawo da hankalinsa kanta yana fad'in." Za su ji in sha Allahu rabbi Hauwa." Tashi na yi ni ma ina dan d'auke kaina domin gabad'aya ba na son kallonsu saboda b'acin rai, duk da kare mana mutuncin da ya yi a yanzu amma na ji haushin yadda suke raha har yana cewa zai je ya yi wa Maryam godiya
 Na furta." Baban Saude ina zuwa yanzu akwai sa'ko da za a kai wa su Dada." Ya ce." To, amma ki hanzarta domin na himmatu." Ban ce komai ba na bi bayan Hauwa wadda na hange ta can bakin kofa tana daf da fita.

Haka muka jera tafiya ni da Hauwa babu magana kamar wasu kurame. Abinda dai ya sanya na k'ara ganin mutuncinta bai wuce yadda ta jure cin fuskar da Baban Saude ya dinga yi mana da farko ba, don gaskiya ya gayyaya mana magana a fakaice. Ni nasan halinsa a ganinsa hakan ba komai ba ne, wai idan ma abinda aka ce masa muna yi da gaske mu ji haushi mu gyara yana yabon Maryam din tare da cewa mu yi koyi da ita. Lallai Hauwa ta yi mini kara sosai duk da nasan ko bata fad'a ba ta ji zafin hakan da farko daga baya kuma da ya fahimci gaskiya har ha'kuri ya dinga bata. Ta yi shiru har ya gama  bata yi yun'kurin ta mayar masa da raddi ba, duk kuwa da cewa lefin ta bai kai a ce an yi mata wannan titsiyar ba, amma ta jure duk domin yi mini kawaici hakan ya sanya ni jin kunyarta kwarai da gaskiya wannan dalilin ne ma ya sanya muna shiga gidan na dube ta a nutse na ce." Hauwa ki yi hakuri don Allah bisa   abinda Baban Saude ya yi da farko haka halinsa yake wallahi. Na kuma gode sosai da karar da ki ka yi mini."
Murmushi kawai ta yi kafin ta furta." Wallahi ko kad'an ban ji haushinsa ba Amina, idan da wanda nake jin zafinsa a raina bai wuce mijinki ba shine ma'kiyana lamba daya, kuma Baban Saude ai ya yi mana abinda iyayenmu suka kasa yi mana Amina, wallahi na tabbatar da cewa ko Inna Uwani na gayawa matsalata bai zama lallai ta dubi gaskiyata ba, shi za ta bawa gaskiya ta d'ora mini lefi, to balle na samu iyayena maza ina nufin 'yan uwan mahaifina wallahi a cikinsu babu wanda zai iya tunkararsa da sunan kwatar mini mutunci saboda yana da kud'i. ai ni Baban Saude ya yi mini kuma babu shaushinsa ko kad'an a cikin raina."

Tana gama fad'in haka sai ta shige dakinta ta barni a tsaye ina bin hanyar da ta bi da kallo. Na jima a tsaye a bakin kofar falon kafin na sauke zazzafar

ajiyar zuciya na kama hanyar d'akina zuciyata cike da nazarin hanyoyin da zan bi wurin ganin mutumin nan ya yi kukan zucci. Idan da hali ma ya yi na zahiri zuciyarsa ta cika da damuwa tunda shi ya sayi hakan da kansa. Yadda ba ya so ana yawon tiritirin kai shi k'ara bayan yana aikata lefi, to ni ma abinda na tsana kenan a rayuwa kuma tun farko-farkon auranmu na gaya masa ba na so ya'ki dainawa. Zai gane idan kai ni kara shine  zai daidaita ni.

Ranar dai gidan na mu tsit ya kasance kowacce tana d'akinta dama ni da Baba ne muke zaman falo Hauwa ba sosai ba kullum tana d'aki a kwance. Tunda na koma na kaiwa baban Saude sak'on su Dada
ban  sake fitowa ba sai bayan magariba Baba ta kammala komai tana zaune ita kadai a falon tana kallo da carbi a hannunta. Gaisawa muka sake yi dalili ita haka dabi'arta take duk bayan sallar farilla sai an yi gaisuwa.
Ban fi minti goma da zama ba Hauwa ta fito da waya a kunnanta tana fad'in." E gata bari na bata sai ku gaisa ." Ta miko mini wayar tana fad'in." Inna ce take magana."
Cike da fad'uwar gaba na amshi wayar ina kallonta taje ta zauna saman kujera
Muka gaisa da inna Uwani cikin kulawa da sakin fuska har muka kare gaishe-gaishenmu ban ji ta yi wata magana ba wanda da farko na d'auka Hauwa ta gaza juriya ta sanar da ita abinda yake faruwa.
Wayar ta kar'ba suka d'an yi magana kafin su yi sallama ta kashe tana kallon baba Tabawa ta ce." Indomin nan nake so Baba duk dai tsugar mini da ciki take yi amma idan ba ita na ci ba na jin dadi. Amma ki hada mini da dankalin turawa ki sanya wadataccen kifi."
Na ce." Hauwa Indomee fa basir ce da atini idan kin manta na tuna miki gashi sai ki ce a sanya mini attaruhu ya ba zata tsugar miki da ciki ba, ki rage cin ta don Allah."

Littafin nan na kudi ne sister kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

"To mai zan ci Amina, ita kadai nake jin sha'awa wallahi ban ta'ba ciki mai azabar laulayi irin wannan ba, da farko fa shiru kamar ba zan yi ba Amma cikin sati biyun nan ina jin jiki k'warai."
Na dube ta sosai ta dashe lebanta duk ya bushe ta ba ni tausayi. Dama kuma can tana da laulayi wannan ne ya yi tsanani.
Baba ta tashi ta kama hanyar kicin din na ce" don Allah Baba Tabawa kada ki biye mata ki sanya attaruhu kad'an kuma kada ta yi da roman nan."
Tana yar dariya ta ce." Haka kuwa za a yi, Hauwa ni ma na daina biye miki gaskiya."
Ta dube ni tana ce wa." Kin san roman shine abinda ma na fi so na dinga lasa dad'i yake yi mini."
Na ce." Mu bar maganar nan Hauwa, ni fa jikina ya yi sanyi ina fatan dai ba ki sanar da inna Uwani wani lamari ba ko."

Girgiza kanta ta yi a hankali ta ce." Babu abinda na gaya mata wallahi, mun yi waya ne mun gaisa ta ce na ba ki wayar ku gaisa."
Ajiyar zuciya na sauke domin har cikin raina na yarda da maganarta.

To a ranar bai shigo mana ba sai da garin Allah ya waye tukkuna ban kai ga fitowa falon ba ya shigo yaran kaf dinsu a tare da shi da yake asabar ce suna gida babu makaranta sai sha biyu na rana suke tafiya tahafiz su tashi shida na yamma.
K'amshinsu ya cika mini d'aki da uban da yaran sun sha gayu. Ido kawai na zuba musu Khalil ya fara gaishe ni kafin sauran suma su tsuguna k'asa kamar yadda suka ga ya yi "Mama ina kwana." Suka dinga jerowa ina amsawa. Khalil din ya ja baya suma sai suka ja baya suka tsaya kusa da shi. Na jima ina nazarin abinda suka yi kafin na furta." Khalil ja su ku tafi wurin Mamanka ku gaisa."
Bai ce mini komai ba sai ya dubi Baban nasu  da yake tsaye a jikin kofa shi bai shigo ba shi bai fita. Ya d'aga masa kai alamar su je can wurin Hauwa.
Na sauke ajiyar zuciya cikin jin d'an sasaauci lallai ya fara sassautowa da d'aukar matakin gyara wata'kila daga haka a hankali yaranmu su dawo a hannunmu.
Da sauri kuwa yaron ya ja su suka fita cike da nishadin da suka shigo da shi.
Ya shigo dakin sosai ya tsaya a jikin mudubi kawai yana kallona Ganin haka ya sanya ni da sauri na tashi na bar wurin, bandaki na shiga duk kuwa da cewa ba ni da wani uzuri, kawai ba ni son kallonsa ne..
Ban fito ba sai da na d'auki kusan mintina sha biyar tukkuna na fito na samu d'akin babu kowa. Tsaki na ja kawai na wuce na je na zauna zuciyata a cunkushe da tunani, ni kam idan ma shiri yake nema a yanzu ban shirya ba domin kuwa ina so na ji dalilinsa na d'auke mini kwanar aure ya kai wa wata, idan ita Hauwa yana ganin babu aure a tsakaninsu, ni ai ba zaman idda nake yi ba. Duk fad'an da za mu yi ya dawo gida ya kwana idan girkina ne. 'Karyar neman tashin hankali yake yi, yanzu ya gama tasa rigimar ni kuma zan yi tawa akan abu biyu yawon kai ni 'kara da yake yi da kuma d'aukar mini kwanar aure, ko ba zai yi komai da ni ba, haka zalika ko ba zai kula ni ba ya shigo dai gidan ya kwana shine magana, ba za a ginu da wannan rainin hankalin ba.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi

amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*1k akan telegram via 0542382124... Binta Umar gtbank*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*100*
Ban yi tunanin zai sake shigowa ba da daddare
muna zaune a falo gabad'aya har da Hauwa wadda take ta fama garzar yalo da Masaudu ya sayo mata can cikin kasuwa. Kamar koyaushe ya tsaya suna gaisawa da Baba Tabawa kafin ya haura samansa. Hauwa ta tarkata shirginta ta nufi daki ba tare da ta cewa kowa komai ba. Girgiza kaina kawai na yi saboda takaici wannan abin da suke yi ita da shi.
Ina zaune ban motsa ba Baba ta ce." Hajiya ko za a hadawa maigidan abinci ne?" Na ce." Ba na jin yana da buk'ata Baba daga gidan matarsa yake."
Ta yi shiru tana kallon wani waje kafin ta sake dubana tana fad'in." Ko za ki tambaye shi dai."
Na ce." Baba kyale shi don Allah, idan yana da bukata daya shigo zai yi miki magana tunda kun dan jima kuna magana kafin ya haura samansa, kin san ba shi da 'koron baki."

Ta jijjiga kanta ba ta sake cewa komai ba sai ta tsirawa tibi Ido nasan ba ta so hakan ba don babu yadda za ta yi ne.
Kashe wayata na yi don ba na so na ga kiransa. Bai sake saukowa ba har muka tashi daga zaman falon baba Tabawa dai babu wani karsashi a tattare da ita muka yi sallama.
Sai da garin Allah ya waye tukkuna na kunna wayar haka na kwana babu sukuni.
Ina bandaki ina wanka na ji motsi ban kawo cewa zai biyo ni bandakin ba kawai sai ganinshi na yi ina tsaye tumbur da ni. Hankalina ya tashi ainun wata kunya mashahuriya ta ritsa da ni. Gani na dinga yi kamar ya keta mini alfarma nan da nan na ji idona ya fara kawo ruwa. Duk da ruwan kumfar sabulun da ya yi wa jikina sansani hakan bai hana ni yin gaggawar raromo towel dina da yake sakale ba. Na fara kici kicin daure jikina tsananin yadda hannuna yake rawa ya sanya towel din faduwa kasan wurin ruwan da yake zuba ta saman shayar da na kunna ya jike shi.
Raina ya b'aci mutuka haka na sunkuya na dau'ko towel ya yi jagab jikina babu kuzari na kashe shayar kafin na ya'ba towel din a jikina a hakan a jike. Ya tsaya kusa da ni a nutse kawai ya zura mini idanuwansa .
Na daure na furta." Amma dai kasan haramun ne abinda ka aikata ko?"
Ya yi shiru bai tanka mini ba kawai dai ya zura mini idonsa kaf ilahirin jikina rawa yake. Can kasa-kasa na yi tsaki tare da d'an janye jikina. Ya sake biyoni har sai da kirjinmu ya hadu. Hannuna ya kamo kafin ya duba tafin hannun kamar mai neman wani abu. Ya cika ya kamo na hagun shi ma yana dubawa. Cike da mamaki nake dubansa Ina nazarin abinda yake yi. Yadda yake sauke ajiyar zuciya shine abinda ya fara d'aga mini hankali.
Ko'karin sanya ni yake yi a jikinsa ina dojewa, na lura lallen da akayi mini shi yake ta bibiko. Kokawa muka fara yi a toilet din  sai kace wasu sababbin amare
har sai da ya cire mini towel din ya yi jifa dashi can gefe, na rasa yadda zan yi da kaina na lura so yake na biye masa mu cigaba da kokaye-kokayen domin ya samu damar ta'ba mini jiki, gabad'aya duka na muzanta
ganina a haka cikin hasken rana ko auratayya zai yi da ni da safe ko da rana yakan sha wuya kafin ya ribace ni na amince domin na tsani ya ga zahiri na a gaske duk da na tabbatar da ce wa babu wata makusa a jikina da za ta janyo mini 'kyama a wurinsa amma haka siddin nake gudun haka.
Saman tumbina da ya dan tasa ya d'ora hannunsa bai ce mini komai ba ya fara wasa da hannunsa a wurin har ya so ya zarce can kasa. Na matse gefe cikin zafin nama kafafuna na wani irin rawa.
Ya sake biyoni a karo na uku. Sai kawai na silale a kasan wurin na zauna tare da takure jikina. Babu wani lamari da zai wanzu a tsakanina da shi a halin yanzu tunda har yanzu ba ni da tsarki kawai dai zai d'aga mana hankali ne.
Ganin yadda nake kuka tukuru ya sanya ya juya ya fita can kasa na ji shi yana fad'in." Ki fito mu yi magana sai mu sake gaisawa."
Bayan ya fita na yun'kura na tashi tsaye har yanzu kafafuna ba su daina rawa ba, sabon wanka na sake yi. Dana kammala na rasa yadda zan yi na fito tunda towel din da zan d'auro ya jike babu wani a toilet din sai 'kananu

kuma babu wanda zai ratsa ni. Na rasa yadda zan yi haka na jure na bude kofar amma ban fito ba ina hangensa a gefan gadona a zauna yana duba k'aramar wayarsa.
"Ka miko mini towel ko zani ka ji."
Ya dago ya dube ni da sauri amma bai ce komai ba, na sake maimaitawa ina janye idona daga kansa. A nutse ya ce." Lallai za ki shekara anan a tsaye idan ni zan miko miki towel Amina."
Jin haka ya sanya ban k'ara cewa komai ba. Na yi kundubalar fitowa haka haihuwar uwata. Da kyar da hard'ewar kafafu na isa wardrobe dina. Ina jinsa yana ce wa." Ni da kayana a ce za a boye mini, to wane lungu da sa'ko ne ba ki kama kaina kin d'ora a wurin ba, da hannunki fa ki ke miko mini idan kin manta wannan kirjin naki cinyesu ne kawai ban yi na taune ba, kina ba ni ina sha fiye da yadda raina yake so."
Ban ce masa komai ba har na gama kintsa jikina yana ta sakin maganganu masu tsananin nauyi wanda na tabbatar da cewa wasu na aikata da sani na, wasu kuma ban san lokacin da na aikata ba domin kuwa bayan ni da shi sai Ubangiji da ya hallicemu ne kadai ya san irin ta'barewa da haukan da muke yi idan muna auratayya."
Na dube shi bayan na juyo da fuskata, gabad'aya yanayinsa ya canza duk ya shiririce idonsa sun risina sun kankance tare da wani irin yanayi. Yana ta ko'karin dannewa amma abin ya gagara. Koda na zauna a gefansa sai ya janyo ni da k'arfi jikinsa na karkwarwa ya fara fadin." Na zata zan iya dauriya Amina, mai zan samu ne, ina ta shirye-shiryen tafiya legos tunda na lura babu tsarki a tare da ke."
Na cire hannunsa da yake cikin rigita a nutse na furta." Ai ba ni da abinda zan iya baka a halin yanzu."
Ya mayar da hannunsa cikin rigar yana fad'in." Ke ce kuwa ki ke da abubuwan bayarwa my love dina."
Na yun'kura na tashi hannun nasa ya sa'bule ya fito daga cikin rigata shi ma ya tashi da sauri na matsa gefe can nesa da shi." Wallahi ba ni da abinda zan baka, ba za ka samu hadin kaina ba muddin ba ka daina had'a ni da iyayena ba, na ga ji da rashin adalcin nan da kake yi mini, ni ba baiwa ba ce, idan kai 'karata shine zai sanya na shiryu to lalacewa zan yi bari ma na gaya maka gaskiya."
Ya zuba mini ido da wani irin b'acin rai a saman fuskarsa ya furta." Haka ki ka ce ko?"
Na ce." 'Kwarai haka na ce, ni da kai, duka babu yaro karami, kamar yadda ba ka so ana tiririn kai ka 'kara wurin magabatanka ni ma haka, ka san halin Baban Saude haka siddin ya zo ya ci wa Hauwa mutunci ai ni ce mai laifi tunda ba ka yarda cikin zubewa ya yi ba, amma ita Hauwa ai taimako ta yi, mai ta yi maka ka saketa kana bin ta da mugun nufi."
Ya jima yana kallona na lura takaici da b'acin rai ne suka taru suka yi masa dabaibayi.

Na ce." Don haka wallahi ni ba baiwa ba ce.''

Yana gyada kansa ya furta." Zuwan da Baban Saude ya yi domin yi muku nasiha ya tashi a banza ko?"
Na ce." Ai kai ma ba jin nasihar kake yi ba, zalinci idan abin yi ka cigaba, ba zan jure ba wallahi."
Ya furta." Wane zalinci na yi miki ba ki da yunwa balle ishirwa ba ki da matsalar sutturar sanyawa, sannan idan kina da bukata ta d'abia ina kawar mini da ita shikkenan ba za ki yi mini lefi na nuna bacin raina ba."
Na ce." Ai na gaya maka ba da gangan cikin ya zube ba, mai yasa ba ka yarda ba har sai da ka kira Baban Saude. Idan ni da kai girma bai sanya mun gyara matsala idan ta taso mana ba to mu cigaba da tafiya a haka ni ba zan gaji ba."
Ya shiru na wani lokaci kafin ya ce." Ni kuma na gaji zaman lafiya nake nema, sannan saboda ba kwa tsoron Allah ke da Hauwa ku bud'e baki ku ce ina dukanku ba ku ji kunyar yi mini sharri ba Amina."
"Ai kaima ka fada ka mare ta, ni ma na gani ta ina muka yi maka sharri."
"To na ji, ke kin manta ta'addancin da ki ka yi mini ko?"
Ya fad'a yana tsare ni da Ido. Shiru na yi tare da zum'bura baki
Ya ce." Ni me yasa ban kai k'ararki ba?" Yafad'a yana juyo da fuskata. Na dube shi ina fad'in." Ai da sai ka gaya masa."
Ya girgiza kansa a hankali cikin sigar rarrashi ya furta." Idan ma kin kashe ni duk a cikin soyayya ce ni babu wanda zan gayawa, amma tsakaninki da Allah na taba dukanki?"
A dan sanyaye na ce." A a sai dai zagi.''
Cikin neman sulhu ya ce." Wannan ma tsautsayi ne da b'acin rai kuma kema kin rama ko kin manta?"
Na ce." Yaushe na zage ka?"
"Ranar da ki ka tura su Yusi kano ki ka ce uban waye ya ce Maryam ta ri'ke miki yara, kin zage ni kin zagi ubana zagin ya yi mini ciwo sosai wallahi."
'Kasa na yi da kaina ganin yadda ya yi kalar tausayi da nadama. Amma duk da haka abinda yake yi din ba zai sanya na janye kudirina ba. Domin mutum ne mayaudari wanda ya iya rarrashi da kalamai idan yana so ya cimma wata nasara."
Ya sake matsowa jikinsa sosai yana ta daga rigar dake jikina. Ya ce.'' Ni yanzu kwanciyar hankali nake nema nafiso mu sasanta kafin ace na koma legos, mu shirya kanmu kin ji giwa komai ya wuce."
Baki na zum'bura na ce." To yanzu ya kake so ayi, ai dama ni ba ni da matsala indai za ka gyara ka dinga adalci ka daina abubuwan da kake yi."
"Na ma gyara tuntuni na kar'bi kuskurena, zan kiyaye." Yafad'a a rikice Yana rungomu kafadata.  Na janye jikina tare da cire hannunsa dake saman cinyata na ce." Shikkenan Allah Ya ba ka ikon yin adalci."
Sai ya yi kasa'ke yana kallona don yadda nake ture shi daga jikina Ina yin baya ya yi masa ciwo. Muka zubawa juna ido ni dashi gabad'aya ya zama kalar a tausaya masa. Mun jima a haka kafin ya gyad'a kansa
bai sake ce wa da ni komai  ya tashi tare da kama hanya zai fita. Cikin zuciya na ce.'' Shikkenan ka ji idan da dad'i, ita matar da ka ratayawa fulawar

soyayya ta iya da kai kawai gabad'aya ni ban ma yarda da nadamarka ba....
✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*2k complete a telegram. What'sapp group 1k*
*0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*101*

Muka cigaba da tafiya a gidan babu annashuwa da jin dad'in da ma'aurata kan jiyar da junansu. Ya sauko sosai ya yi tubis da shi domin salon horon da na d'auka ba karami ba ne.
Gashi har yanzu bai cewa Hauwa komai ba dangane da zamanta a gidan domin da ya mayar da auransu a k'alla zai samu jin sau'ki ta 'bangaranta. Ya mayar da ita bai mayar da ita ba Allah ne masani, suna dai zaune a haka ita tana wasan 'buya dashi shi kuma yana nuna mata isa da iko irin na d'a namiji tabbas ko bai fad'a ba nasan jiranta yake ta kai kanta ita kuma girman kai ya hanata ta lallaba ta bashi ha'kuri. Amma yadda yake ta kokarin ganin mun zauna lafiya ni da shi na tabbatar da cewar ya d'auki shawarwarin Baban Saude domin ya rage wasu abubuwan sosai da yake yi mussaman akan yaran. Ba su dai dawo gidan ba, amma a sati sukan shigo sau uku ko hud'u mussaman ranar juma'a muna yini tare da su uwar rik'on na su ta had'o su da kayayyaki masu yawa wai su kawo mana. Ban iya cewa su mayar mata ba domin ita Hauwa kallo ba su isheta ba, kusan ni nake diban turarukan ni ma kyautarsu nake yi sauran na ce Baba Tabawa ta yi amfani da su. Ban ta'ba tambayarsa yaushe zai dawo mana da yaran gabad'aya ba, kawai na zuba masa Ido domin ganin iya gudun ruwansa
Yadda na ri'ke wuta nake watangaririya da rayuwarsa abin har mamaki yake ba ni. A tsukin Allah Ya jarabce shi dani ainun, ni kuma na'ki bada dama yana ta dai lallaba ni domin idan ma ya yi fushin bai wuce na kwanaki biyu zuwa uku ba zai sauko ha'kuri kuwa ya ba ni ya fi a irga. Dad'i nake ji na ganshi yana karyar mini da kansa sai na yi ta tuna irin rashin mutuncin da ya dinga tsuga mini a can baya.
Matar da ya ratayawa fulawar so dama can ita  ba wani kwanciyar aure yake yi da ita ka'in da na'in ba da bakinsa ya gaya mini hakan ba matsa shi na yi ba.Ashe ni da ya mayar towon tushe nice marufar asirinsa domin kuwa tuntuni ni nake iyawa da fitinarsa ko Hauwa ba za ta nuna mini komai ba.
Dama tuntuni na gama fahimta cewa ta wannan sigar ake gane rauninsa domin babban abinda yake daga masa hankali ya zo da buk'ata naki amincewa ko kuma idan muna yi na'ki taimakawa da wasu abubuwan da za su ba mu nishadi bakidaya hakan ma na kara rikita shi sosai

Gabad'aya ya nune koyaushe ya shigo gidanmu ba shi da wani kuzari tafiyarsa Legos ta dinga tangal-tangal domin ya turza-turza da ni na'ki amincewa da na bi shi, na gaya masa har abada kafata ta sake taka garin nan, idan lallai sai na yi zaman auran da shi to ina nan."
Saura kwana daya ya tafi Lagos din ya ritsa ni a d'aki. Da farko rarrashi ya fara yi da ban baki tare da alkawarin ba zai sake kai ni kara ba. Kamar koyaushe hakan bai sanya ni na sassauto ba domin kuwa a duk lokacin da zan daga kaina na kalleshi wallahi duhunsa nake gani, a ganina zamana a gidansa kamar takura kai ne  tunda shi kam ai kansa ya sani, idan ma ya ce ya tuba da tafiya tayi nisa sai ya koma ruwa
Bai wani ba ni tausayi ba duk kuwa yadda yake rausayar da kansa da muryarsa hakan bai burge ni ba. Da ya lura duk abinda yake yi ban saduda ba sai fad'a ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba. Har da cewa ba zai

ka'ra nema na ba har ya mutu na je za mu tsaya a gaban Allah ranar lahira idan har yana da hakki mala'iku za su yi mana sheda domin kuwa ba zai ta'be yafe mini hakkinsa ba.
Ban damu ba ina zaune ina kallonsa ya kama hanya ya fice cikin b'acin rai.
Sai bayan fitarsa kuma na ji wani iri a jikina a lokacin da yake had'a ni da Allah. To ban san yadda zan yi na huce takaicin da ya jima yana kunsa mini ba, kuma ni so nake ya gyara tunda ya zame mini takalmin kaza, ba zai yiwu ya saba take mini hakki ya kwana lafiya ba, Ubangiji zuciya yake dubawa domin ba ni da k'arfi ta kowane bangare sai ta wannan hanyar itace damata kuma hanyar da za ta sadudur masa da jikinsa gabad'aya.

Da zai tafi ko sallama bai yi mana ba, sai da ya kwana uku ma da tafiya tukkuna muka samu labari a bakin Masa'udu cewa ya tafi ban ji komai a jikina ba, dalili na riga nasan irin rabuwar da muka yi ta rashin arziki ba zata bari ya shigo ya yi mana sallama ba.

***
To kwanaki suka cigaba da tafiya har aka fara lissafin watanni da tafiyarsa bai kira waya ba haka zalika mu ma ba mu kira ba. Cikin zuciyata nake fad'in mai hali baya fasawa, aka ce idan ka kwana biyu baka ga mutum ba idan kun hadu to ka tambayeshi halinsa.
To sai na so tsokanar Hauwa tukkuna zan ce mata ta kira shi a waya ta ji yana lafiya. A lokacin zan ga b'acin ranta ta dinga fad'in mijinki dai Amina, ki daina danganta ni da wannan rikitaccen tsohon. Na yi ta dariya idan tana hayaniya a raina nakan ce jinin jikinku kuma yana yawo a junanku tunda duk rintsi a ba za a canzawa towo suna ba.
Babu wata ala'ka da ta sake had'a mu da Momi, tun bayan abubuwan da suka faru. Sai dai ko bayan tafiyarsa ba ta fasa turo mana yara ba, itama Hauwa ba ta sake maganar dawowarsu ba ban san abinda yake cikin zuciyarta ba kuma yanzu.

Wannan littafin na kudi ne Hajiya kada ki karanta mini ba tare da kin biya ni hakkina.

Har yanzu kadaran kadahan nake jin ta a zuciyata. Kuma ba na jin haushinta ainun sai dai irin kishin nan da ba za a rasa ba. A ko'ina zan fad'a alheri ta yi mini don yara sun shiga tsakaninmu hakan ba zai sanya ni na mance ba. Na dai nesanta yarana da ita shikkenan sai a zauna lafiya.
Sosai Nusaiba da Salim suka d'auki gaba matsananciya da mu. Adam ne kawai yake iya daurewa idan tsautsayi ya sanya mun had'u ya gaishe ni, amma tun ranar da su Yusi suka bar garin gabad'aya ya gaina shigowa gidanmu. Salim da 'yar uwarsa Nusaiba kam abin na su ya yi nisa idan za mu had'u sau goma cikinsu babu wanda zai dubi inda nake balle na sanya a raina cewa za a gaishe ni.
Yusi bai ta'ba gaya mini ce wa Adam ya ziyarce shi har sau biyu ba duk kuwa da cewa yakan kira ni a waya sa'i da lokaci mussaman a ranakun da ba su da

makaranta tunda tuntuni sun cigaba da d'ora karatunsa a bayaro  wasu lukutan ba su da isheshen lokaci mussaman Kamalu da ya ri'ke b'angare biyu. Karatu yake yi sosai irin na da'awa sosai yake bin Malam sunna domin samun ilimi kwanaki satinsa guda a Bauchi wurin Sheikh Guruntum. sai bayan da ya dawo tukkuna yake gaya mini da na tambaye shi dalili ya ce mini yana zuwa  neman fatawa ne. Yanzu dai yana tare da Shaikh Abdullahi gadon-k'aya yana daya daga cikin yaransa da suke take masa baya.
To a bakin Hamusu nake samun labarin zuwan Adam din don har yake gaya mini irin kayan da Momi din ta aikawa da Gwaggo ta hanyar Adam din.
Na yi mamaki sosai kuma jikina ya kara yin sanyi da lamarinta a yi alheri da kyauta hannun hagu bai sani ba. Duk yadda na nuna mata rashin 'kara da kawaici akan yaran nan k'okarinta zumuncin nan da take ta nanata mini ya cigaba da tabbatuwa.
Ubangiji Allah Ya ba mu ikon yin abu dominsa.

Haka dai rayuwar ta cigaba da tafiya a hangunce ta fannin maigidan namu kam yadda ba mu neme shi ba shima bai neme mu ba. Tun abin baya damuna har ya fara damuna sai na fara fargabar kada ya sanar da Baban Saude cewa ga abinda na tsiro dashi dukda akan gaskiyata ne, to amma nasan ba ni da hujja Mai karfi idan baban Saude ya titsiye ni dalilin abinda ya sake nake haka Koda na gaya masa dalili zai ce mini Mai yasa ban fad'a masa ba ranar da ya zo ya sasantanmu tunda kafin ya tafi sai da ya dinga tambayarmu idan da wata matsalar mu fad'a bayan wadda muka gaya masa.
Ga bikin Fadila babbar diyar anti Yagana ya tashi. An yi bikin Yusura sati shida da suka gabata lokacin muna tsaka da rikici dalilin da ya sanya ma kenan ban tambayeshi ba domin kuwa nasan zai huce fushinsa akan hakan ya samu damar gasa mini maganar da ransa yake so kuma ya hana ni zuwa, saboda kada dukan ya zama biyu ya sanya na k'yale shi.
Hajja da kanta ta kira ni a waya game da zuwa bikin Fadila da suke shirye-shiryen tafiya ita da Gwaggo tare da yaran wato su Kamalu ai anti Yagana mutuniyarta ce don haka ban yi mamakin nuna za'kuwarta akan sha'aninta ba. Rasa abinda zan ce mata na yi na kama inda-inda da kyar dai na ce mata ni ma ina nan ina shiri amma wata'kila za su riga ni yin gaba. Ba ta fahimci cewa da matsala ba muka yi sallama na ajiye waya cikin zullumi da tunanin yadda zan sanar da shi tafiya maiduguri ya bar ni kai tsaye. Da kunya kusan wata hud'u da tafiyarsa ban kira shi ba bayan kuma nasan da tsananin fushina ya tafi yanzu kuma na kira shi nace masa me?"
Haka  kwana biyun nan na kasance cikin yanayi na tunani har sai da Hauwa ta fahimta ta tambayeni na gaya mata halin da ake ciki. A lokacin itama jikinta mutuwa ya yi ta dinga fad'in lallai a wannan ga'bar baki da bakin magana Amina. Bikin Fadila kuma ai ke ce kirjin biki, idan ba ki halarta ba akwai matsala gaskiya.
To katsam ina cikin wannan halin ya zo ba tare da tsammanin zuwan nasa ba, tunda ka'ida wata shida muke yi a can legos din mu dawo, wai ashe Momin ce babu lafiya hawan jini da sugar har sai da ta kwanta a asibiti tsayin kwanaki goma ba mu sani ba, na yi mamaki sosai domin yarana suna zuwa

dukda a satin bai fi sau biyu suka zo ba amma babu wanda ya gaya mana. Kenan a hannun masu aikinta yaran suke har ta fito daga asibitin ko da yake dama sune suke dawainiya da su Mairo da Taburni yaran suna yawan kiran sunayensu
Masa'ud shi ya gaya mana wannan labarin domin kuwa shi din ma ya tabbatar mana da zuwansa kamar yadda ya tabbatar mana da tafiyarsa. Bai shigo mana a ranar ba sai washe gari da rana wajan daya da minti biyar lokacin ma daka gani daga massalaci ya fito.
Muna falo gabad'aya muka yi masa barka da zuwa ya amsa kadaran kadahan babu fushi haka zalika babu cikakkiyar walwala. Ya tsaya suna magana da Baba Tabawa kamar yadda suka saba har yana ba ta labarin rashin lafiyar Momi din da yadda ta ji jiki. Sosai ta dinga jajantawa tana k'ara tabbatar masa da cewa gabad'ayanmu ba mu sani ba. Wannan karon Hauwa ba ta tashi ba ban sani ba ko nauyin da jikinta ya yi mata ne oho, tunda cikinta a cikin wata na takwas yake ya fito sosai idan ta jibge a wuri d'aya da kyar take tashi. Ya kama hanyar samansa babu wadda ya sake kalla a cikinmu. Amma yanayinsa kadai ya tabbatar mini da cewa lalurar da matarsa take ciki ta dame shi saboda ga yanayin yadda yake bawa Baba Tabawa labarin ciwon tabbas ya ci jikinta da k'arfi.
Bayan shud'ewarsa daga wurin da kamar minti goma na tashi na bi bayansa zuciya cike da zullumi da fargaba.
A kwance na same shi kawai ya tsirawa rufin d'akin ido. Gabad'aya sai gwiwa ta yi sanyi (wai shin me cece ma duniyar nan ne) tausayinsa ya d'an kamani, amma bari tasirin hakan ya raunarta da ni ba. Har yanzu da sauran takaicinsa a cikin zuciyata.
A nutse na zauna gefan k'afafunsa. Ya dube ni bai ce komai ba sai ya janye idanuwansa. Na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." Wallahi ba mu san ta yi ciwo ba, ashe har kwanciya ta yi a asibiti babu labari ai da mun shiga mun dubata."
Ya yi shiru bai ce mini komai ba. Sai na janye idona daga kansa na yi kasa da kaina ina dan wasa da yatsun hannuna. Shiru d'akin ya yi na minti kusan goma kafin na sake dubansa yanzu idonsa a lumshe yake kamar mai shirin bacci ganin haka sai na tashi da niyyar fita. Ba tare da ya bud'e idon ba ya ce." Koma ki zauna ina son magana dake....

*Yau fa mutumin ko ni ma ya ba ni tausayi 😆😢 Amina a sassautawa Babanmu mana.*
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: ☘
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai

magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*2K COMPLETE ON TALGRAM.*
*VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*102*
Na zauna din kamar yadda ya buk'ata. Ya tashi zaune tare da sauke k'afafunsa kasa. Ya dube ni a nutse kafin ya furta." Akwai matan da annabin rahama ya fad'a cewa ya gan su a can karkashin wutar jahanama, kuma suffofinsu sukan bayyana tun a duniya. Akwai kuma matan da tun a duniya za a dinga yi musu ishara da nuni da cewar aljannar Firdausi madawamiya ce a gare su. Sune muminai wad'anda ayyukan alherinsu yake bayyana ga ko'ina."
D'akin ya yi tsit bayan ya gama maganarsa. Na dube shi tare da furta." Ni ina a wane babi kenan, ko kuma na ce a wane ajin ka ajiye ni ai ba kai kake bada aljannar ba."
"Tabbas ba ni nake bada ita ba, amma tana k'asan kafafuna haka annabin rahama ya fad'a."

Na jima ina dubansa da mamaki wato yabi duk hanyoyin da zai raunatar mini da zuciya bai ci galaba ba shine ya fara wa'azi. Ni abin ma dariya ya so ya ba ni, Ashe ya sani yake takewa da yake hakkinsa ne, ashe da ciwo kuma babu dadi.
Na daure sosai kafin na furta." Ayyukana ba su kai ka daga mini kafarka ba kenan?"
Ya gyada kansa yana ce wa." Gaskiya ba su kai ba har yanzu. Momi ce ko yau ta fad'i ta mutu wallahi na yafe mata ki shaida aljanna da izinin Allah zata tabbata a kanta."
Na yi shiru zuciyata tana hantsilawa saboda tsabar bala'in b'acin rai. Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un na cigaba da nanatawa ban sake mayar masa da martani ba, kuma ban tashi daga wurin ba na ji gyaran muryarsa yana cewa." Kwanaki mun yi waya da Hajja take sanar da ni za su tafi maiduguri da yaran zuwa hidimar bikin 'yar anti Yagana hakane ko."
Ban dube shi na ce." Hakane yau saura kwana tara, jiya dai Hajja take ce mini ranar alhamis za su tafi."

Shiru ya d'an ratsa wurin kafin ya nisa ya sake ce wa." Yanzu nawa ki ke ganin zamu ba su gudumawa ni dake?" A takaice na furta." Duk abinda Allah Ya hore maka."
"Ai shawara na tambayeki ni Allah Ya hore mini tuntuni. Kawai ki gaya mini abinda za a ba su ai auran fari za su yi ko."
Na kalle shi babu sukuni na furta." Ya za a yi na yanke maka abinda za ka bayar, ai ba kudina ba ne, naka ne, kuma dai daidai gwargwado sun yi hidimarsu ni ma kuma tuntuni na tura mata da tawa gudumarwar abinda ka ga dama shi za ka ba su."
Ya gyada kansa yana fad'in." Ok na ba su 5m ya yi ko?"
"Idan haka ka yi niyya ni ina ruwana?" Na fad'a tare da d'auke kaina domin har ga Allah zuciyata zafi take yi mini game da irin mummunan fatan da ya gama yi mini yanzu.
Ya ce." Kada ki gaya mini magana Amina, ba na son rashin kunya da fitsara ko kin ga na ta'ba jikinki ne, kin ga alamar sha'awarki a k'wayar idona, ina ce wannan shine yake kawo mini raini a wurinki to ki ri'ke kayanki ba na so."
Na fashe da kuka tare da cewa." To ai dama ban ce ka nemi shawarata ba ni ma, kuma ban ce ka neme ni ba, abinda ka yi niyya shi za ka yi, ni ma abinda na yi niyya shi zan yi, aljanna dai kuma babu wani bawan da yake bada ita ta Allah ce, ta hanyoyin alheri ana samunta ba sai ta dalilin wani ba."
"Na ji abinda ki ka ce ta shi ki tafi."
Na tashi haka kawai na tsinci kaina da buga siket din da yake jikina na kama hanyar fita raina a masifar 'kuntacce.
Ban sauka ba tukkuna sai da na daidaita yanayina na sauka na same su suna nan a wurin suna hira Hauwa hannunta ri'ke da apple tana ci babu abinda ya dame ta sai addu'a da ko'karin rabuwa da cikin jikinta lafiya.

Ban zauna falon ba kai tsaye d'akina na nufa na yi zaune zugum a gefan gado zuciyata na ta yi mini sa'ke-sa'ke masu kyau da marasa kyau! Lallai cikin wannan duniya babu komai face rikici da tarin kalubale.
Babu yadda ban yi ba da Hauwa akan ta shirya bayan magriba mu shiga mu duba Momi amma fafur taki tace itama abar dubawa ce domin kuwa bata kaita jin jiki ba. Ganin taki fahimtata ya sanya na kyaleta kawai muka shirya da Baba Tabawa muka tafi dubanta.
A harabar gidan muka riski Salim da Adam a tsaye suna magana. Da sauri shi babban ya d'auke kansa yayin da karamin ya sassauta a nutse ya dube mu da ladabi yake fad'in." Mama ku ne."
Na ce." E, mune Adam mun shigo duba Momi ne. Sai ya yi yar dariya wadda babu annashuwa a cikinta ya furta." To shikkenan mu je na yi muku jagora."
Gaba ya yi muka bi bayan shi yayin da Salim din yake ta ciccin magani har da jan tsaki. Murmushi kawai na yi a zuciyata gabad'aya yaron ma ni tausayi yake ba ni, domin kuwa ya d'auki lamarin da zafin gaske.
Falo muka zauna ya nufi bedroom din ta yana fad'in ."Bari na sanar da ita." Ba mu kai minti biyar da zama ba daya daga cikin masu aikinta ta fito daga kicin da wata madaidaiciyar roba a hannunta Hassana da Minal suna biye da ita. Ganinmu a zaune ya sanya yaran suka tsaya. Ita kuma mai aikin ta karaso wurin da muke har sai da ta risina kafin ta gaishe mu gabad'aya.

Ina kallon yadda Baba Tabawa take jan yaran da wasa da tsokana amma suna can nesa da mu sun tsaya suna ta kallonmu kamar sun ga dodanni. Duk da akwai sabo a tsakaninmu dalilin shigowar da suke yi amma ganinmu a gidan sai ya zame musu wani banbarakwai
Raina ya 'baci nan take zuciyata ta dinga raya mini abubuwa marasa kyau to idan ba an zauna da yaran an fadi wata magana ba mai zai sanya k'ananun yara irin wad'annan su dinga yi mini wani irin kallo. Abin b'akinciki da takaici ma har da 'yar cikina 'kiri-'kiri saboda kin gaskiya.
Idona na zare musu sosai na ce." Tsayuwar ta mecece idan ba za ku gaishemu ba to ku daina kallonmu, ko mun yi kama da tibi ne.''
Matashiyar mai aikin da take jigila da su tana dariya ta furta." Ke Hassana ku zo ku gaisa Mama ce fa."
Na ce." A'a rabu da ita kada ta zo mu gaisa ta tsaya." Usaina ta fito daga kicin da shafceciyar wuk'a a hannunta tana fad'in." Mairo ga wukar ki yanka mana." Shiru ta yi tana kallonmu yayin da mai aikin ta je ta da sauri ta kar'bi wukar tana fad'in." A can sama fa na d'orata yanzu Usai sai da ki ka d'aukota."
Ba ta ce mata komai ba ta nufo wurin da muke zaune tana zuwa sai ta dora kanta a cinyata tare da zura yatsanta babba a baki tana tsotsa. Na yi shiru ina sauke ajiyar zuciya yayin da na d'ora hannuna a saman kanta.
Ganin haka ya sanya Hassana da sauri itama ta zo ta yi yadda Usainar ta yi dama tuntuni Kamalu ya gaya mini kishi ne da su, duk abinda daya tayi to babu shakka yar uwata ma sai ta yi. Da hannu na yi wa Minal alama ta zo wurina. Ta kuwa taho kataf-kataf domin yanzu itace take tashen ki'ba a

cikinsu.  Na ri'keta sosai Ina fad'in." Ina Khalil yake?" Cikin yanayin maganarta ta furta." yana can gidan anti Nusaiba."
Baba Tabawa sai murmushi take yi tana jan su da wasa. Hassana da Usaina iyayen miskilanci ne, Minal din ta fi su sakin fuska da son mutane. Tunda suka dora kawunansu saman cinyata babu wadda ta dago sai da suka ji muryar Babansu tukkuna.
Tare suka fito da Momin kallo daya na yi mata gabobin jikina suka shika wata irin rama ta yi mai ban tsoro kanta yana nema ya rinjayi gangar jikinta abinka dama da siririya idanuwanta sun yi kuru-kuru ta d'ashe k'warai da gaske ta yi fau, babu shakka babu k'arya a cikin lalurarta yadda mijinta ya dinga jadadda ciwon ya ci karfinta yanzu na sake gazgata kammaninta duka sun canza ta hadu da ciwuka masu hatsarin gaske sugar da hawan jini.
Ta zauna tare da taimakonsa suka zauna kujera d'aya yana dan gyara mata 'kafafunta ko daga inda nake zaune Ina kallon yadda jikinta yake rawa.
Ban ji haushinsa ba ko kad'an domin a yanzu dai babu maganar kishi ga matar da take cikin irin wannan yanayin na halin ciwo mai tsanani. Ta dinga fara'a a zahiri tana nuna jin dadinta. Muka gaisa cikin kulawa da mutunci. Na yi mata sannu da jiki haka zalika ma baba Tabawa ta dubata sosai. Ta dinga dariya ganin yadda twin's suka yi mini farincikinta ya kasa 'boyuwa ta ce." Ai maigidan yake gaya mini ba ku ji labarin na kwanta a asibiti ba, ku yi hakuri don Allah da yake ni kaina lokacin ba ni hayyacina sai da na kwana na yini tukkuna na fara gane wanda yake kaina. Ko da na tambayi Nusaiba da Nabila shin an sanar daku suka ce mini eh sun sanar daku halin da ake ciki, na gode sosai Amina Allah Ya bar zumunci."
Cikin nutsuwa da kulawa na ce." Allah Ya sawwa'ke yasa kaffara ne amma maganar gaskiya babu wanda ya gaya mana cewa baki da lafiya balle mu ji cewa kin kwanta a asibiti na tsayin wannan kwanakin." Na yi shiru Ina mayar da numfashi kafin na cigaba da cewa." Tabbas da mun sani me zai hana mu zuwa asibiti mu duba ki, babu niyyar wulakanci ko kuma nuna wariya a tsakaninmu dake kuma ciwo ake ce kin ga kuwa lalura ta kori komai, Ubangiji Allah Ya sawwa'ke, Hauwa ta ce a duba ki da kyau kuma tana yi miki sannu da jiki itama kwana biyu da yake ta yi nauyi sosai ba ta jin dad'i ne."
Yanayinta ya nuna alhini da damuwa a zahiri abinda ta nuna kenan. Sai ta gyad'a kanta a hankali ta ce." Babu komai Amina komai ya wuce kuma na ji sau'ki sosai wallahi sai dai rashin 'kwarin jikin da yake d'an damuna yanzu, a cewa da Hauwa ina amsawa Allah Ya raba lafiya."
Na ce." Za ta ji in sha Allahu rabbi."
Tun kafin mu yi sallama take yi mini godiya har sai da jikina ya mutu tsabar tausayin halin da take ciki. Mairo ita ta janye yaran ta tafi dasu tana yayyanka masu mangwaron da tun farkon shigowarmu suke he rigima a kansa....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *2k ON TALGRAM*
*VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*

*V-VIP AREWAPEN*
*Wsp Gruop 1k*
*103*
Duk abinda muke yi bai ce mana komai ba, mun dai gaisa amma tun bayan gaisuwar bai sake magana ba, sa'i da lokaci dai yakan amsa waya idan an kira shi.
Misalin takwas da wani abu muka fito daga gidan tun a hanya muke alhinin yanayin da muka risketa Baba Tabawa dai kasa daurewa ta yi a hanyarmu ta shiga gida ta fashe da kuka da sauri tasa gefan jihabinta ta rufe fuskarta . To ni ma dai kukan zucci nake yi domin na shiga rud'ani ba karami ba ganin yadda Allah Ya mayar da baiwarsa. Idan kudi na sayan lafiya nasan da ba wannan maganar ake yi ba. Wannan da duniya ta yi mata sheda cewa mutuniyar kirki ce wadda tun a duniya mijinta ya ce ya yafe mata itace cikin irin wannan yanayi to ina ga wanda ya shure umarnin Ubangiji kuma, Ubangiji Allah kasa mu dace Amin.
A haka muka shiga gidan Hauwa na kwance saman kujera 3str tana kallo abinta. Ganinmu sukuku ya sanya ta tashi zaune tana tambayar lafiya.
A takaice na ce." Lafiya lau." Na shige d'aki domin yadda kafafuna ke rawa ba zan iya tsayuwa a wurin ba. Na zauna gefan gado tare da rafka tagumi wani abu ne ya zo ya tsaya mini a wuya na tsananin fargaba da tashin hankali mace ta koma sai kace mai cutar kanjamau! ko mai farfadiya sai an rirriketa. Hawaye suka fara sauka a kumatuna. Haka kawai na ji duniyar ta fice mini daga raina gabad'aya.
Shigowarta ya sanya na daga kaina na dube ta. Ta zauna gefana babu babu fallasa ta ce." Ashe kema kukan ki ke yi Amina." Sai ta sa dariya kafin ta cigaba da cewa." ga Baba Tabawa can ma tana yin nata, ni kam matar nan ko dame take yawo wallahil-azim kurwata tafi tata d'aci, wallahi ni zan yi maganinta."
Na gyada kaina ina ko'karin ture kutittiran abinda ya tsaya mini a wuya na ce." Hauwa k'ullaci da tsananta gaba da k'iyayya wallahi babu inda zai kai ki sai tashar dana sani. Matar nan dai duk rashin Imanin mutum ya ga halin da take ciki sai ya tausayata mata don Allah mu dinga sassautawa kanmu Hauwa."
Ta ja tsaki tare da furta."lalura fa kowa yin ta yake yi, wallahi na fita jin jiki, ni mai yasa ban lanjare ba, saboda ba ni da hakkin kowa a kaina, ita kuwa bari na gaya miki abinda ta shuka ne take girba tun a duniya hakkin mutane ne wallahi."

Na jima ina kallonta tare da auna maganganunta.  Yadda take tabbatar da abinda ba ta da tabbas akai shine abinda ya fi daga mini hankali da lamarinta. Wace irin kiyayyace wannan. A ganina wannan abin da take yi jahilci ne tsantsa da rashin sanin abinda ya dace. To ba ni da bakin magana domin kuwa yadda ta yi nisa irin haka babu wani kalami da zan yi mata ya sanya ta sassauto daga irin kiyayyar da take yi wa matar nan wadda alherenta suke dabaibaye damu bakidaya.

Ganin ban ce mata komai ba ya sanya ta tashi tana fad'in." Matsantawa kai ne kawai kowa ya kashe wutar gabansa. Shi kuma ai hakkin rai tun a duniya Ubangiji yake fitar da shi wallahi tallahi yanzu ta fara gani.

Sai kawai na saki bakina ina kallonta har ta fice daga d'akin ban d'auke idona ba.
Na jima a zaune Ina tufkewa da warwarewa kafin na tashi jiki a sabule na shiga bandaki domin watsa ruwa a jikina. Gabad'aya cikina ya cushe babu dandano a bakina ko kad'an yunwar ma sam ba na jin ta, daga zarar na tuna halin da muka riski matar nan a ciki sai hankalina ya tashi.
A haka na shirya cikin kayan bacci ina tsaye gaban madubi ina busar da gashin kaina. Ya turo kofar d'akin ya shigo. Ban yi zaton shigowarsa ba. Muka had'a Ido ya nufo wurin da nake tsaye daf da ni ya tsaya na gama abinda nake yi yana ta kallona ta madubi na juyo kirjinmu ya hadu waje daya. Kusan a tare muka sauke ajiyar zuciya. Ya riko hannuna muka zauna gefan gado. Yanayin fuskarsa kadai shi ya nuna mini cewar ya ji dadin abinda na yi. Ya furta." Kin kyauta sosai kuma na ji dadin abinda ki ka yi, idan haka kuke yi mini kara akan abinda nake so mai zai sanya ni ma na 'bata muku ai babu abinda ya fi zaman lafiya dadi ko."
Kanzil ban ce masa ba. amma maganarsa ta d'an dake ni wato shi baya jin nauyin gaya mana irin son da yake yi wa matar nan tasa.
Ya d'ora hannunsa a tudun kirjina wanda tun zaman da muke yi a wurin hankalinsa yake kai. Ya nisa kafin a kasalance ya furta." Momi ba ta da lafiya Amina cikinta da wajenta wallahi, tausayinta nake ji sosai domin lalurai sun gama dabaibayeta."
A nutse na furta." Allah Ya yaye mata, da sauran al'ummar musulmi."
Ya amsa da Amin kafin ya dora da cewar." Kin san yanzu wani result din ya sake fitowa bayan gwajin da aka yi mata satin da ya wuce cancer bakin mahaifa."
Da saurin gaske na dube shi. Ya gyada kansa "Wallahi ni kaina na kad'u Amina na tausaya mata k'warai da aniya  yanzu haka za mu yi booking domin zuwa india akwai kwararrun likitoci a can da za su caje mini ita sosai."
Jiki a masifar sanyaye na furta." Tabbas Ubangiji shi yake saukar da ciwo ya kuma saukar da maganinsa, ina yi mata fatan alheri tare da addu'ar samun lafiya madawamiya, kai kuma Allah Ya baka ladan jinya."
Ya sake amsa da "Amin Ya Allah." D'akin ya d'auki shiru har yanzu hannunsa na saman kirjina yana dan tattabawa. Ban hana shi ba kawai dai ina mamakinsa ne a ganina yanayin alhinin da yake ciki da damuwa akan rashin lafiyar maid'akinsa bai kamata a ce wani abu na jin dad'in duniya yana bijiro masa ba, to mai ma zai fahimta bayan yana cikin tashin hankali a haukana fa kenan
Na dube shi yana lumshe idonsa kamar wanda ya samu audiga na dan ture hannun nasa muka kalli juna a sa'rke na ce." Dama ina son magana da kai."
Kai tsaye ya furta." Idan har akan zuwa maiduguri ne to kada ki bata bakinki babu inda zakije....

Na kudi ne littafin don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na ce." To saboda me, kafi kowa sanin matsayin anti Yagana a wurina ko?"
Ya gyad'a kansa a tsanake ya ce." Da dai ban rantse ba ne sai na bari ki je, amma wallahi na riga na rantse ki yi hakuri bayan bikin sai ki je ki ga d'akin amarya."
Zuciyata ta dinga tiriri na dinga danne abinda yake yun'kuro mini domin ba ni son na nuna masa damuwata a kan haka a gaba ya samu abinda zai k'untata mini idan wata matsalar ta faru a tsakaninmu. Na gyada kaina tare da furta." Shikkenan mu ajiye wannan maganar ina so ka gaya mini matsayin zamanka da Hauwa a gidan nan, domin ni har yanzu na kasa gane abinda kuke nufi da kai da ita."
Ya dube ni sosai kafin ya ce." Ke ina ruwanki kuma?"
Na ce." Ni ce kuwa nake da ruwa tunda duk wata mas'ala da kuka samu da kai da ita a kaina ne, yanzu a matsayinka na babba mai hankali da jagoranci abinda kuke aikatawa daidai ne."
Ya ce." Ai taki ta amince da cewar ta yi lefi, sannan taki ta bi umarinina idan tana so magana ta shige mai yasa bata biyo ki zuwa duba Momi ba. Ta cigaba da zama a haka duk ranar da ta gaji sai ta nemawa kanta mafita."
"Gaskiya hakan ba daidai ba."
Ya 'bata rai yana fad'in." To nuna mini daidai Amina."
Shiru na yi ban sake magana ba. Ya ja tsaki yana fad'in." Na yabe ki sallah za ki kasa alwala, Hauwa ai ba yarinya ba ce idan tana son zama da ni ta ba ni ha'kuri ta kuma bi umarina."
Na ce." To ai kaine babba ha'kurinka shine zai fi rinjaye."
"Na yi iya wanda naga zan iya yi a kanta Amina, wannan ya zama na farko ya kuma zama na karshe, kada ki sake titsiyeni akan lamarin Hauwa ko ni din sa'anki ne?"
Shiru kawai na yi Ina kallonsa. Ya cigaba da ce wa." Dangane da maganar kwanan aure kin ga Momi bata da lafiya ya kike ganin za a yi?"
Na ce." Yadda muke yi mana."
Sai ya yi shiru yana tunani kafin daga bisani ya furta." Shikkenan sai a cigaba da tafiya a hakan, zan kwana biyu ban koma legos ba, domin idan na kai ta asibitin na dawo zan dan jinyaceta."
Uffan ban ce masa ba, ya tashi tsaye yana kallona cikin sigar kulawa ya furta." Ki same ni a sama zan shiga in yi wanka." Ban iya ce masa komai ba har ya fita daga d'akin Ina zaune zuciyata ta kasa tsayuwa wuri d'aya.
A daran na gurzu a hannunsa k'warai da gaske kamar wata sabuwar amarya sai da na yi ruwan d'umi domin kusan sau uku ya yi mu'amula da ni. Farkon dare da asuba bayan ya dawo daga sallah. Still Yana gama breakfast nan ma ya sake yin wani haka na sauko daga saman a galabaice.  Na yini ciye ciyen kayan da zasu saukar mini da ni'ima domin na tabbatar da cewar a wannan daran ma ba zai daga mini kafa ba..

***

Bayan kwana biyu da misalin biyar na yammar ranar talata muka yi ba'kuwa a gidan. Hajiya Aziza sunanta matar abokinsu ce Alhaji Sulaiman duk dai abotar tafi karfi tsakaninsa da Alhaji Amadu mai rasuwa dalili shi da girmansu suka hadu ba abotar kuruciya ba ce. Sai bayan rasuwarsa tukkuna abotar ta maye gurbi akan shi da yake ba ni labari. Uwargidansa ce kuma tare suke da maigidan sun zo duba jikin Momi ne tunda ko bayan rasuwar Alhaji Amadun suna yin zumunci dalilin da ya sanya ma kenan Alhaji Sulaiman din yake binbinin abotartasu ta yi karko kamar yadda ta yi da Alhaji Amadun. Shigowarta kenan ya kira wayata ya yi mini wannan bayanin wai ta ce za ta shigo ta gaishe mu kafin su tafi yanzu shi suna tare da maigidan nata a can gidan Momin.
Na ce masa in sha Allahu babu matsala. Sosai na marabceta na sanya Baba Tabawa ta kawo mata abinci tana fad'in a 'koshe  take ta ci abinci kafin ta fito nace ta daure ta sanya mini albarka.
Hauwa ta fito suka gaisa sama-sama cikin rashin sakewa ta koma dakinta. Na kira Baba Tabawa domin ta zo ta kwashe kayan abincin da ta jera wanda kad'an ta ci daga ciki. Duk da babu sabo a tsakaninmu amma na lura tana da kirki kuma ta girme mu gaskiya zata iya yin sa'a da Momin ina tambayarta yara ta ce suna nan lafiya biyu suna d'akin mazajensu kenan ta auran da yara biyu akwai hud'u a gida uku maza sai 'yar autarsu mace. Su uku ne a wurin maigidan ita ce Uwargida.
Ta ce." Ai na ga yaran a can gidan Hajiya Maryam twins sun yi wayo sosai sun zama 'yan mata, Ubangiji Allah Ya yi musu albarka."
Na amsa da amin Ya Allah, ai kam duk sun yi wayo."
Ta gyada kanta da d'an murmushi a fuskarta kamar wadda aka tsikara ta ce." Allah dai ya sawwa'ke abinda ba zai shige ba ni Hajiya Aziza."
Kallonta na yi ban ce komai ba. Ta sake yin murmushi kafin ta ce wani abu kira ya shigo wayarta tana d'agawa na ji tana fad'in." Halisa har na fito ma daga gidan, a alhamdulillahi jikin nata da sauki wallahi, eh na gaya mata sa'konki ta ce ta gode." Ta yi shiru tana sauraranta kafin ta ce." To ya za a yi lalura aka ce fa Halisa kin kyauta ai Allah ma yana son masu wannan zuciyar irin taki Ubangiji Allah Ya sa mu fi karfin zuciyarmu."
Daga can ta amsa da Amin kafin su yi sallama da juna ta dube ni tana fad'in." 'Kanwata ce Halisa.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *2K ON TALGRAM.*
*VIA  0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*104*
*Whasap Gruop 1K*
Na ce."Allah sarki a takaice ina d'an wani nazari a zuciyata sai na ji maganarta tana fad'in." Halisa k'anwata ce cikinmu daya ai da da rabo kuma Allah Ya yi wa Alhaji Amadu tsayin rayuwa suna tare da Maryam din domin kuwa sun yi soyayya k'warai kuma har iyaye suka shiga maganar har da

yarjejeniyar aure a tsakani domin sadaki ne kawai bai biya ba lamarin ya rushe.
Shiru na yi ban ce mata komai ba. Ganin haka ya sanya ta cigaba da ce wa."
Alhaji Amadu ya so Halisa sosai kuma ya yi mata hidima k'warai farko a gidana suka had'u ya nuna yana sonta sanin halin tsananin kishin matarsa ya sanya da maigidanmu yake sanar mini da buk'atar abokinsa na ce a a gaskiya dalili na farko Maryam k'awata ce muna zumunci sosai saboda abotar mazajenmu. Duk da ba mu zaune a gari daya amma muna ziyartar junanmu sa'i da lokaci kuma muna yin zumunci ta waya bayan haka kuma tsaye take a kan yarana kamar yadda ni ma nake tsaye akan yaranta. Shiyasa ban yi mamakin ganin yaranku a gidanta ba domin zahiri macace mai son yara da gaske da hidima su.
Da yake 'yar kasuwa ce mai zafin nema ba zan manta ba tasha yi mini fad'a sosai idan muka hadu tana fad'in ko ba zan nemi kudi don yarana ba dalilin ubansuya tara musu na tashi na nema domin iyaye da 'yan uwa da kuma gajiyayyu.
A duk lokacin da wani abu ya fito na ya yi muddin ta yi odarsa to kamar yadda za ta d'ibarwa Nusaiba kaya haka zata d'ibarwa Asiya da Madina kaya irin na yarinyarta babu bambamci ko kad'an. Sosai take yi mini kara akan komai ni kaina na sheda tana da kyauta da kirki daidai gwargwado Maryam duk wanda ya ra'be ta zai dandali arzikinta. Sai dai kin san an ce d'an Adam tara yake bai cika goma ba nasan dai tuntuni Maryam ba ta son kishiya tasha gaya mini a rayuwarta abinda tafi tsana kenan dalilin da ya sanya lokacin da maigidanmu zai 'kara aure ta dinga ba ni shawarwarin yi masa tutsu da wasu dai shawarwarin da nake ganin za su iya kaini ga halaka. Lokacin na tsananta da addu'a sosai domin mu gaskiya gidanmu gidan malamai ne Amina ba mu ta so mun ga iyayenmu na yawon bin malamai ba. Addu'a dai da yin nafilar tsakiyar dare ita iyayenmu suka koya mana tare da azkar a duk lokacin da wata matsala ta tunkaro mana. Gaskiya ban yarda na bi sharwarin da take ba ni ba na dai dage da addu'a sosai akan idan auran da mijina zai yi akwai alheri ina rokan Allah Ya hada ni da abokiyar zama tagari dalili tunda?a na ta so gidanmu mata hud'u ne a ciki kuma mahaifinmu tsayayye ne da wuya ma a cikinmu wata ta kaso auranta ta dawo masa gida da zumar yin zawarci daidai gwargwado mun samu kula da tarbiya.
Sosai Alhaji Amadu ya makance da soyayyar Halisa ya zama duk bayan sati biyu daga nan abuja sai ya je Jigawa gidanmu hira wurin Halisa a lokacin itama bai kwanta mata a rai ba ta zo tana gaya mini abinda yake faruwa ni lokacin ma ban san yana zuwa zance ba tunda mun gama magana da Babansu Madina akan zai gaya masa cewa ta tsayar da wanda zata zaura kuma gaskiya ne akwai wanda suke soyayya a lokacin sai dai bai kai ga turowa ba, Amma dai gidanmu sun san da maganar mahaifinmu ma sun yi magana da mahaifinsa akan hakan.
Na dinga mamaki sosai sai dana tambayi Babansu Madina akan mai yasa bai gaya masa ba sai yace ya gaya masa ya'ki ha'kura ya ce tunda har yanzu shi wancan din bai fito ba shi ba zai janye ba.

Na kira ta zo  na ce da ita duk lokacin da ya sake zuwa kada ta fito ta yi masa kora da hali domin a gaskiya ba ni son abinda za a yi shi daga baya rai yana b'aci Muna mu'amula da Maryam sosai a tsukin na tabbatar da cewar ba ta san abinda yake faruwa ba, kuma ba na son abinda zai ta'ba zumuncinmu. Idan lallai ya zama dole mijinta ya kara aure to ya nema a wani wurin amma ba daga b'angarena ba.
Sati uku da yin wannan maganar ta  sake zuwa gidana tana kuka sosai ta ce mini ya sake zuwa kuma Babanmu ya saurare shi. Wata dabi'a ce ta mahaifinmu son bawa mai aure d'ansa. Ni kaina don dai lokacin da maigidan nan ya fito da niyyar aurena da gaske yake domin gabad'aya ya shigo da na tabbatar da cewa mai mata Babanmu zai bawa ni. tana gaya mini sun yi magana sosai da Babanmu har ya ce ya jira shi zai yi magana da iyayen Murtala saurayin da suke soyayya idan har da gaske yake yi to ya fito a cewarsa masu son auran da gaske suna fitowa ba za a ce za a zauna jiran wani lokaci ba.  A lokacin shi Murtala din baya gari ya tafi can kudu Benin suna harkar gwangwani.  Amma ya ce mata yana dawowa zai yi magana domin a zo a kawo kudin aure. Da ta gayawa Baban namu haka ya ce sai ya ji ta bakin mahaifin Murtala din  tukkuna zai yanke hukunci.
Dole ta ha'kura ta tsaya sauraransa. Lokacin Malam Shu'aibu  bai rufe komai ba ya gayawa Babanmu cewa. Har yanzu Murtala ba shi da taku daya wanda idan ya yi aure zai ajiye iyalinsa. Can kudu (Benin) da yake zuwa tare da abokansa sana'a suke yi ta inada da 'karafuna da robobi, wannan shine amma tunda manemi ne arziki na Allah ne. Shi ba zai hana idan mijin aure ya fitowa yarinya ta yi auranta ba domin tauye hakki ne a ce mace ta zauna jiran namijin da bai zama lallai ya yi mata adalci a gaba ba, tunda da yawa hakan ta faru samari su yi alkawarin aure da budurwa su tafi neman kudi idan sun samo sun dawo gida sai su ga ai sun fi karfin ajin wannan budurwa da suka bari a gida.
Wannan maganganun na Malam Shu'aibu maihaifin Murtala ya zaburar da Babanmu a cikin satin da Alhaji Amadu ya je gidan namu suka yi magana ya ce idan har da gaske yake kuma ya shirya auran ya  turo magabantasa. A tak'aice dai Amina na gaya miki da ni da Halisa sai ji muka yi an kawo kudin auran dubu dari biyun  shekarun baya mai d'anko. Kuka sosai Halisa ta zo gidana ta na yi mini kamar ranta zai fita tana fad'in ita kwata kwata bai yi mata ba tsoho ne. A lokacin da take wannan koke-koken babu abinda nake tunani sai yadda za ta zauna da Maryam domin na fi kowa sanin yadda ta k'yamaci kishiya a rayuwarta.
Sosai na tausheta da rarrashi da ban baki har Babansu  Madina ma da ya dawo ya sanya bakinsa yana ta kwarzanta mata nagartar abokin nasa yana fad'in ta kwantar da hankalinta ta yi mijin da za ta yi alfahari da shi. Muka rarrasheta sosai ta ha'kura kwanta uku a gidan namu da yake duk gari daya muke gidan iyayenmu na kazaure gidana kuma a dutse a kwana na hudun Alhaji Amadu ya zo gidan  wata'kila ya je can gidanmu aka ce masa tana nan
 lokacin da rarrashi da ban baki na tursasa Halisa sauraran Alhaji Amadu suka dan jima a d'akin bakin maigidan suna hira kafin  su yi sallama ya tafi ta

shigo mini da kwalin waya sabuwa dal black berry mai kyau da tsada da kudi dubu hamsin wai kudin zance.
Na taya murna sosai a lokacin na kuma bata sharwari akan ta dage da addu'a domin duk lamarin da Babanmu ya kar'be shi da hannu biyu to tabbas ya yi istahara a kai ya gano alherinsa don haka idan tace zata tayar da fitina za ta fita zakka a cikinmu tunda ba ita kadai aka ta'ba yi wa irin haka ba.
Sannu hankali soyayyar Alhaji Amadu ta kar'bu a zuciyar Halisa yadda shi ma yake hidima da ita da gidanmu na tabbatar da cewa da gaske lallai auranta zai yi domin duk bayan sati biyu ko kwana goma yake zuwa wurinta har aka tsayar da maganar daurin auransu wata shida farkon watan maulidi.

Abinda ya fi tsaya mini a raina dangane da al'amarin shine yadda mu'amulata da Maryam bata raunana ba na shiga mamaki sosai jikina kuma ya yi sanyi k'warai na tabbatar da cewar duk wannan abinda yake faruwa Maryam bata sani ba domin kuwa da ta sani dole zan ga canji daga wurinta dalili kuwa shine na fi kowa sanin abinda tafi kyama kenan kishiya. Na gayawa Babansu Madina cewa ni fa hankalina gabad'aya bai kwanta da neman auran nan ba, domin kuwa ina zargin abokinsa da munafurtar uwargidansa. Da ya tambayeni mai yasa nake zargin hakan na ce masa naga ko kad'an ban ga canji a wurinta ba muna zumunci sosai domin ma a satin da aka sanya ranar daurin auran ta aikowa da yara kaya kowanne set biyu da muka yi waya ta ce mini sabuwar order ce shine ta d'ibar musu.
Shi kansa ya jinjina al'amarin sosai amma daga lokacin bai kara tayar da maganar ba ni ce dai abin ya dame ni a zuciyata domin sai nake ganin kamar duk ranar da ta san abinda yake faruwa za ta yi mini kallon munafuka ko kuma mai sonta kanta, ba kuma zata ta'ba yarda da cewa mijinta ne ya ga Halisa yace yana so ba za ta yi zargin cewa ni ce na had'a su.
Wallahi na shiga damuwa sosai da sosai domin kuwa ga'barar da Alhaji Amadu ya d'auka ta neman auransa ba mai kyau ba ce a ganina yafi alheri ya fito ya gaya mata akan ya 'boye mata.
Na kasance cikin zullumi da tunani a koyaushe nazarin da nake yi shine idan har Maryam ta samu labarin mijinta zai auri k'anwata wane kallo za ta yi mini.
Katsam watarana na ga text message d'inta ina dubawa na ga ta rubuto mini Aziza na gode sosai ashe tsakanina dake ba zaman amana, kema kin boye mini abinda yake faruwa, na d'auka ni dake yanzu mun zama 'yan uwana na ji don kin gaya mini mijina na neman auran k'anwarki Halisa menene ko kin d'auka zan tsananta kishi a kanta, ai abin gudu a kishiya shine a d'auko maka kwarkwasa wadda ba ka san ni ba, amma ni kam na sheda halinki kuma ina fatan haka Halisa take da kyawawan halaye idan har da akwai alheri a zamana da ita Ubangiji Allah Ya kawota cikin gidana, ke kuma na gode da 'boye mini da ki ka yi."
Jikina ya yi sanyi sosai da na gama karanta sakon data turo mini na zauna ina ta tunani da mamaki. Dama nasan tuntuni ba ta san abinda yake faruwa ba sai yanzu da daurin auran bai wuce wata biyu da kwanaki ba sannan ta

samu labari. Hakika kowacce aka yi wa haka dole zuciyarta ta sosu Amma sai na dinga mamakin yadda ta sadada har ta samu damar yi mini text kuma cikin nutsuwa bata kalubance ni akan had'a baki muka yi da mijinta ba.
Na kwana da tunanin hakan a raina sai da gari ya waye tukkuna na kira ta a waya ta daga babu jinkiri muka gaisa sosai cikin ko'karin kare kaina na fara yi mata bayanin abubuwan da suka faru tun farkon neman auran har zuwa yanzu. Ta dinga fad'in ai na d'auka ni dake babu rufi Aziza babban abinda ya ba ni haushi kenan yadda kike biye masa kema ki ka yi mini shiru wato sai dai kawai na ji an d'aura auran kenan kun yi mini adalci.
Na shiga bata ha'kuri da tausarta Ina nuna mata cewar ban san ta yadda za a yi na iya tunkararta da maganar ba domin ni duk a tunani na mijinta ya gaya mata.
Ta ce mini bai gaya mata ba ita ta fahimta da kanta yana neman aure da kuma ta yi bincike ta gane Halisa ce k'anwata.
Yadda muka fahimci juna sosai a wayar ya sanya mini kwanciyar hankali da nutsuwa a zuciyata na amince da cewa Maryam ta sakko ta kuma yi na'am da  cewa kishiya abokiyar zama ce kuma hukuncin ne na Allah....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *07084653262*
Wallahi Amina duk yadda na so da ganin na sakar mata jiki kasawa na yi duk tsananin sabon kuwa da yake tsakaninmu sai ta dinga ba ni tsoro daga zarar na kalleta sai na tuna irin mawuyacin halin da Halisa ta shiga. Duk da zato zunubi ne amma tsakani da Allah kenan na fi gazgata cewa itace ta jefi Halisa ta kuma juyar da hankalin mijinta akan lamarin gabad'aya. Haka nan muka yini da ita kadaran kadahan domin hausawa suna cewa idan ba ka iya kama b'arawo ba shi sai ya kama ka shiyasa kawai na kyaleta ban iya ce mata komai akan lamarin ba tunda ai a duniya muke akwai kuma ranar tsayuwa idan har ita ta cutar da Halisa ta d'ora mata muguwar jinyya mai wahala ubangiji zai fitar da hakki.
Muka rabu kowa zuciyarsa cike da tunani domin kuwa ko bata fito ta fad'a tabbas ta fahimci na canza mata ba kamar yadda muke a da can baya.
Lokacin da na gayawa Babansu Madina zuwanta da kayan da ta kawowa Halisa da yara ya yi godiya kawai daga haka bai sake cewa komai ba Amina kin san su maza ba su yarda da irin wannan muddin ba gani suke yi a zahiri ba domin da farko da na gaya masa nuna zargin Maryam akan ciwon dake damun Halisa ya dinga fad'a yana cewa shikkenan lalura ba zata samu bawa sai a jingina hakan da wani mutuniyar kirki ce wadda ba ta da abokin fad'a sam baya tsammanin za ta aikata haka.
Duk yadda na so na fahimtar da shi ya kasa fahimta nagartatta kawai yake fadi shi ma ya sheda ayyukan alherinta a zahiri.
To sai kawai na kyale shi domin ba zai yarda ba zai ce muna neman tayar da fitina ko mu had'a shi da abokinsa.
Tun daga ranar da ta zo taga sauyi a tare da ni sai ta janye jikinta itama. Amma ba gabad'aya sa'i da lokaci tana kirana a waya mu gaisa ko kuma na

ga aike mussaman idan zata turo kaya garin nan to za ta had'o da sakon yara mai delivery ya kawo mini har gida. Duk shekara kuwa idan ta fitar da zakka tana turo mini ta ce na duba family din mu wanda suke da k'aramar sana'a na ba su domin su tashi da kafarsu. Wannan shine zan fad'a akan Maryam Amina amma ban ta'ba zarginta akan dukiyarta ba dalili nasan macace mai zafin nema mussaman a lokacin da iyayensu suka rasu ya kasance girma ya hau kanta duk itace take tsaye a kan 'yan uwanta kuma mijinta ya tsaya mata sosai har ta kafu kwarai ta tsaya da k'afafunta ko a lokacin da muke mu'amula sosai nasan tana da manyan shaguna uku daya a garinsu biyu a garin Abuja. Amma yanzu labarin da nake ji a tsakanin matan abokan mijinmu ta mallaki wurare da yawa a rassa daban daban da ake mata hurd'a ta kasuwanci. Lokacin da na samu labarin auranta da Alhaji Tajo na yi mamaki sosai ya aka yi ta amince da zama dashi a matsayin ma'aurata bayan yana da iyali ita kuma da bata son kishiya. Sai babansu Madina yake gaya mini wasiyyar da Alhaji Amadu ya bari kenan amma ba zan boye miki ba wallahi na shiga tashin hankali ganin da na yi mata a yau sai na ji gabad'aya duniyar ta fice mini daga rai lallai d'an Adam ba a bakin komai yake ba. Dama na sanar da Halisa kafin mu zo shine fa ta ce idan har na zo na ce tana gaisheta da sannu da jiki wallahi lokacin da nake gaya mata sakon Halisan sai hawaye shaaa suka sauka a kumatunta har na yi danasanin gaya mata ta ba ni tausayi sosai lallai Allah ya jarrabeta da ciwo mai wahala muna ro'kon Allah Ya bata lafiya ya kuma yafe mata kuskuranta."
Ajiyar zuciya na saki a hankali na ce." Amin suma Amin, muna nema mata afuwa da sasaauci wurin Allah, ai d'an adam sai dai idan ba hallice shi a duniya ba Hajiya amma tunda annabawan Allah suka kuskurewa Ubangiji kowane bawa ba zai tsallake ba, sai dai mu yi addu'a akan Allah Ya sa kada son zuciya ya sanya mu cutar da wani tabbas ban so jin wannan labarin ba wallahi ba zan boye miki ba hankalina ya tashi amma komai dalili yake yi. Momi ta aikata abu mafi muni shirka shine had'a Allah da waninsa cutar da wanda bai ji ba kuma bai gani ba. Idan na ce miki ta yi mana wani abu mai razanarwa na yi mata sharri domin ni dai a zamana da ita ban hangi wani babban lamari kwatankwancin na Halisa ba. Kamar yadda kika fad'a macace mai alheri domin ta ri'ke mini yarana da ubansu ya rasu don 'karamin ma ya fi shekara shida a hannunta babban ne bai wani jima ba wani dalili ya katse zamansu a hannunta. Idan kin ce ta gwanance wurin kissa da kisan mummk'e wannan zan bada sheda akan haka domin halin da muke ciki kenan da ita koda take kwancen nan maigidan hankalinsa yana wurinta kuma tsayin zamansu gaskiya bai ta'ba kawo mana wani korafi ko aibu a kanta ba asalima boye sirrinta yake yi ko fad'a suka yi ba ma ganewa. Gabad'aya ya za'be ta ya fifita akanmu. Kuma kin ga ni dai a zahiri mun fita kuruciya da komad'a amma wallahi a kanta ko 'ya'yanta sai ran kowa ya 'baci a gidan nan. Ni matsalata da ita kenan. Amma ta fanni asiri ni ban yi imani da cewa jifanta zai yi tasiri a jikina ba koda tana yi din wallahi ba a zaune nake ba nima ina ko'karin kare kaina da addu'a da neman tsari. Ban 'ki ba shi maigidan domin a wasu lukutan abubuwan da yake yi kamar mai rangwamin hankali. Amma duk ba wannan ba yanzu ta lafiyarta ake yi domin sai da

lafiya ake komai.  Duk abinda muke zargi ko hasashe a kanta idan har tana aikatawa muna roka mata gafara daga wajan Allah mu ma ba mu wuce mu tsinci kanmu akan hanyar da ta bi ba ba mu da wayo ko dubara sai ta Allah. Allah ya yafe mata da mu bakidaya."
Ta amsa da Amin Ya hayyu ya 'kayyymu, ai in banda na zo na ga halin da take ciki hankalina ya tashi wallahi babu wani dalilin da zai sanya na tashi maganar nan in banda yanzu kin ji babu wanda na ta'ba zama da shi na gaya masa sai dai zargi da hasashe da mutane suke yi a kanta, sannan da wasu maganganu da na ji ana yi a kan ku wai kun had'e mata kai ba ku sanyata a cikinku kun wareta kin san maganar duniya bata 'buya shine fa abin ya ba ni mamaki cikin zuciyata nake fad'in yadda nasan Maryam da wayo da kissa anya za ku iya kai ta 'kasa kuwa."

Da mamaki mai yawa na ce." A a wallahi ba mu ware ta ba sharri ne kawai irin na mutane amma ke don Allah a ina ki ka ji wannan maganar."
Tana yar dariya ta furta." Wallahi a gari na ji ni ma shine nake ta mamakin Hakan saboda nasan Maryam ba zata ta'ba yarda ta yi boranci a tsakaninku ba."
Na girgiza kaina da damuwa mai yawa na ce." Aikuwa masu fad'in haka sun d'auki hakkinmi ba mu ware Maryam ba wallahi, sharri ne kawai irin na mutane idan an ce babu jituwa a tsakaninmu na yarda amma babu maganar mun had'e mata kai ko mun ware ta."
Ta ce." Allah Ya kyauta dai yanzu gashi Halisa yaranta hud'u fa a gidan Murtala shine ai nake cewa Allah ya tsine abinda ba zai wuce ba."
Kafin na bud'e baki na yi magana suka shigo su biyu maigidan ne da mijin nata Alhaji Sulaiman. Sai yanzu na sheda fuskarsa lokacin haihuwar twins da ya shirya walima na gan shi ya zo da kuma lokacin d'aurin auransa da Momin na ga hotonsu a tare ashe shine.
Suka iso wurin da muke zaune Alhaji Sulaiman din ya fad'in." Uwargida ta gidan Tajo ina 'yar uwar taki take ne?"
Ina d'an ya'ke na ce." Hauwa tana ciki ba ta jima da tashi ba, ina yini ya hanya mun gode sosai fa."
Ya ce." Ai ta ce  za ta shigo ku gaisa ina can tsaye ina jiranta kusan minti talatin me kuka tattauna ne?"
Ya kàrasa maganar da barkwanci sai na yi dariya ganin mutum ne shi mai raha ba irin abokin nasa ba na ce." Hira muke yi ta duniya idan kana so ku ji abinda muka tattauna sai ku gaya mana abinda kuma ku ka tattauna a waje."
Sai kuwa ya fashe da dariya yana dukan kafadar abokin nasa kamar wani kurma yana tsaye yana kallonmu cikin dariyar dai ya ce." Ka ji fa mutumina to mu ai ba zai wuce sabgar kasuwanci muka tattauna ba ko ba haka ba ne?"
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Ita fa kishi ne da ita shiyasa take  bugun cikinka ko tana tunanin aure zan 'kara."
Hajiya Aziza ta yi caraf ta ce." A haf yanzu gashi babu wanda ya matsa bakinka ka fad'a abinda yake zuciyarka kenan zaka kara aure tunda ya baka labarin yana neman cike gurbi ko."

Yasa dariya yana cewa." Wallahi ya gaya mini kuma wai budurwa ko?''
Ta ce." Budurbazar dai ba budurwa."
Sai suka fashe da dariya a tare. Na yi sakato da baki Ina kallonsa yadda yake ta kyalkyala dariya yana tambayar Hajiya Aziza wai menene budurbazar ita kuma tana ta jin haushi domin daka ga ni da gaske mijin nata auran zai yi kuma budurwa."
Yana dariya ya dube ta yana fad'in." Ke in banda abinki ai abinda ake ya yi kenan kuma tsoho da kudinsa sai ya sha shagali ko ba haka ba ne mutumina."
Alhaji Sulaiman yana gyara babbar rigarsa ya ce." 'Kwarai kuwa Alhaji to menene sunna ce fa mai karfi kuma iyayen yaran nan ma yanzu sun fi so su bawa irin mu aure."
Na ce." Makwad'aitan iyaye ba, amma gaskiya kuna da budurwar zuciya kai fa har jikoki ne da ka, amma shine za ka d'auko musu magana."
Maimakon maganata ta bashi haushi sai ma ta bashi dariya tunda na lura mayen dariya ne tunda ya shigo bakinsa a bud'e yake ya ce." To shine me? Amina daga kawai ina da jikoki uku sai aka ce na tsufa a ah ni yanzu ji na nake yi kalau da ni wallahi."
"Um!" Kawai na ce na juyar da kaina gefe abin yana damuna. Ko dai Shima neman auran yake yi ne ganin ba a tambaye shi ba ya fallasa asirin zuciyarsa. Wata zuciyar ta ce mini a a hankalinsa fa yana kan matarsa ba ma shi da nutsuwar duba wata mace da sunan aure matarsa da yake tsananin so bata da lafiya. Anya wannan hasashen na zuciyata ya yi daidai kuwa.
Na ji maganarta a tsakiyar kunnena tana fad'in. " Amina za mu gudu kuma ba ki ba ni lambar wayarki ba. Da sauri na dube ta sai na ganta a tsaye tana gyara jakarta dake rataye a kafadarta.
Na mike tsaye da sauri ina fad'in." Har tafiyar ta tashi kenan, to mun gode sosai Ubangiji Allah Ya ba ku ladan ziyara da dubiya." Ta amsa da Amin tana miko mini wayarta. Na karba na sanya mata lambata ba don raina ya so ba dalili na fahimci tana da surutu idan ba haka ba mai zai sanya daga zuwanta babu wanda ya tambayeta ta fara zuba. Gabad'aya ma ni sai na ji zuwanta bai yi mini dadi ba na farko labarin da ta ba ni akan Momi ba wai na k'aryatata ko na gazgatata ba, nasan hakan na iya faruwa abin ya tsaye mini a rai ainun! sai kuma wannan wasan da ya kasance wanda suke daukarsa kamar barkwanci ni kuma abin ya d'an sosa mini rai wata'kila da gaske shima neman auran yake yi kuma budurwa tunda gashi abokinsa yana fad'a mutum da kudinsa kuma iyayen yara yanzu sun fi so su bawa mai aure yaransu a ganinsu za a fi kula da su.
Iyakacin rakiyar da na yi musu bakin kofar falo lokacin ma dab ake da kiran magriba. Shi ya bi su a baya ni kuma na koma ciki kai tsaye d'akina na shiga na zauna gefan gado tare da tallafe ha'ba. Oh hasashen da ake ta yi akan matar nan yana nema ya zama gaskiya tabbas akwai abinda take yi ko ta sanya malamanta ke yi mata akan jama'a, ai 'yar kasuwa ce mai hurd'odi da yawa mafi akasari kuwa duk eani dan kasuwan da ya yi shura a duniya yana neman jama'a walau ta hanyar Allah ko ta hanyar halaka. Ni dai nasan ina tsananta rokona ga Allah akan ya kawo mini kasuwa da jama'a masu k'aunar

abinda nake sayarwa ko a can baya ma da na dinga fafutukar tsayuwa da kafafuna addu'ata kenan Allah ka d'ora ni akan masu sayan kayana, Ubangiji Allah ka haskakani Allah ka ba ni nasibi da jalabi abinda nake roka kenan a wurin Allah ban ta'ba kauce hanya domin tara mutane ta kowace siga ba. Tabbas ana neman jama'a ana kuma karawa da farin jini da kwarjini babu shakka akwai daya daga cikin abu biyun nan da na fad'a tana yi ko kuma tana sanyawa a yi mata. Asirin mallaka kuma za ta iya yi masa tunda labari yazo akan cewa ba ta son kishiya idan ba mu fita ba to ita ta fita zakka a cikinmu ta zama mad'aukakiya a wurinsa. Wannan shine tunani na akanta.

Bayan sallar Isha'i ya shigo ban ji ma da idar da sallah ba ina ma zaune saman daddumata da carbi mai lamba makale a hannuna. Sai da ya jira na kammala tukkuna muka shafa addu'a a tare ya ce." Abinci za ki ba ni yunwa nake ji wallahi tun safe rabona da abinci  Amina."
Ina ninke dadduma ban kalleshi ba na ce." Tun safe lallai da ka sani kawai ka d'auki azimi."
Ya d'an riko gefan hijabin jikina cikin sigar tsokana ya furta." Idan na yi azimi ke kanki kin san gajiya nake yi da daddare ba ni iya aikata komai kuma yau na jarabtu dake."
Ya'ke na yi ban ce komai ba. Ya sake janyo hijabin nawa a karo na biyu har sai da na yi tangal-tangal na ce." Menene hakane?"
Ya cika gefan hijab din yana fad'in." Je ki kawo abincin mu yi magana."
Ban ce komai ba na fita kai tsaye kicin din na nufa Baba Tabawa ta gama shirya komai jallof din shinkafa ta yi ta ji alayyahu da busashen kifi ta yi kyau sosai tana ta kamshi ta had'a zobo shima da ya ji kayan kamshi Baba Tabawa akwai tsafta da gwanancewa wurin shirya abinci mai rai da lafiya. Na shirya masa duk abinda ya kamata a tire na d'auka na fita daga kicin da takaicin abubuwa da yawa a raina.
Yana kwance saman gadona yana waya na dire tire din hannuna tare da zama can gefe ya d'an jima yana wayar kafin ya kammala ya sauko kasan kafet yana fad'in." Ki zo mu ciyar da juna mana."
"Ka ci kawai zan ci an jima."
Bai sake magana ba ya zuba abincin da kansa bai nemi dana zuba masa ba lemon ma shi ya tsiyaya abinsa ya yi Bismillah a nutse ya fara cin abincin. Na d'auki wayata ina dubawa sai na tsinkayi maganarsa yana fad'in." Hirar me kuka yi ne da Aziza Amina?"
Ya fad'a tare da dubana. Na kalleshi da mamaki namiji da son jin gulma kai tsaye na ce." Hirar matarka muka yi.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: Ya ce." Hirar matata kuma?"
Na ce." E, mun yi hira akan lalurarta da kuma wata mas'alar da ta shafe ta.''
Ya d'an kalle ni kafin ya mayar da hankalinsa kan abincin da yake gabansa ya furta." Ku fa mata ba a raba ku da gulma Amina wace mas'ala kuma?"
Da mamaki na ce." Ka ji ka da wata magana ai yanzu gulma ta tashi daga kan mata ta koma kan maza wallahi."

Ya kalle ni na wani lokaci kafin ya ce.'' To ba ni na sha wace mas'ala ce?"
Yadda ya fadi maganar cike da son jin labarin sai ya ba ni dariya sosai na ce."
Ka gani ko? dama na gaya maka gulma ta tashi da ka kan mata."
Sai ya 'bata rai yana cewa." Me ki ke nufi ?" Nasa dariya tare da cewa." Ai ban ce maka magulmaci ba misali na yi kawai."
Murmushi ya yi kafin ya cigaba da cin abincin d'akin ya d'auki shiru na wani lokaci  na ji gyaran muryarsa na dube shi ya gama cin abincin ya ta so ya zo kujarar da nake zauna ya nani'ke ni sosai yana fad'in." Bari na zauna kusa dake sosai zan fi fahimtar gulmar yadda ya kamata."
Murmushi na yi ban ce komai ba. Ya kamo hannayena yana dubawa kafin ya ce." Wai ke ba ki jin kunya ne?"
Na kalleshi da sauri kafin na ce." Me kuma na yi maka?"
Ya bud'e tafukan hannayensa yana fad'in." Ya kamata ace hannayena da naki sun bambamta ki dinga yin lallai na gaya miki yana yi mini kyau."
A jiyar zuciya na d'an sauke a nutse na ce." To zan yi in sha Allahu.''
Wayarsa aka kira ya je ya d'auka daga tsaye ya amsa kiran na d'an wani lokacin kafin ya kammala yana kashe wayar yake fad'in." Lokacin madam ne yanzu kashe wayoyin zan yi gabad'aya sai Allah Ya kaimu kuma."
ina kallonsa ya kashe duka wayoyin nasa kafin ya dawo ya zauna kusa da ni yana cewa." Ba ni labari."
Sosai na dube shi kafin na ce." Kasan Halisa k'anwar Hajiya Aziza?"
Ya d'aga kansa yana fad'in." Kwarai na san sunanta amma a zahiri ban ta'ba ganinta ba.
Na gyada kaina a sanyaye na furta." Labarin abinda ya faru da ita ya ta'ba mini zuciyata."
Sai ya ce." Ta ba ki labarin Alhaji Amadu ya ta'ba nemanta ne?"
Na ce."E, wallahi, amma yadda aka kusa sabauta mata rayuwa shine abinda ya rikita ni, kai Allah dai ya yafe mana."
Cike da rashin gane inda na dosa ya ce." Shikkenan kuma saboda Allah bai kaddara an aureta ba sai a sabauta mata rayuwa komai yin Allah ne fa, tabbas na ji labarinta wurin alh Amadu lokacin jim kad'an da rasuwar matata ta biyu Ayush ba na gari ma yake gaya mini yana neman auran kanwar Aziza matar Alhaji Sulaiman daga baya kuma ya ce mini ya janye saboda wasu dalilai."
Na ce." Bai gaya maka gaskiya ba matarsa ce ta jefe ta ta d'ora mata muguwar jinyya mai razanarwa."
Ya gyad'a kansa kafin ya furta." Abinda ta gaya miki kenan?"
Na ce." Kwarai kuwa, Kuma gaskiya akwai 'kamshin gaskiya a maganarta domin wallahi zan gaya maka  a sammace kake Maryam ta gama da kai."
Dariya ya fara yi yana kallona kafin ya furta." Ai ni kafin ki ga mace ta gama da ni wallahi sai ta yi da gaske Amina."
Na ce." Au haba?''
"K'warai kuwa, yanzu dai mu bar wannan maganar mu yi ibada domin mu samu lada."

Na ce." Magana fa ba za a bar ta ba, saboda kasan gaskiya Hajiya Aziza ta fada shiyasa kake bagarar da maganar wallahi ko ka 'ki ko ka so Maryam mashirika ce."
Da sauri ya ce." Subahanallahi!"
Na juyar da kaina gefe na ji yana fad'in." Ki daina  ba ni so ranar lahira Ubangiji ya tsayar mini dake domin ki bada sheda shin kin ta'ba ganinta tana shirka da Idonki."
Na girgiza kaina a hankali kafin na ce." Ban ta'ba gani ba ayyukanta ne suka nuna haka a zahiri."
Jim ya yi yana nazari kafin ya ce." Kin ga wad'annan maganganun Amina na jima ina jin su akanta tun kafin ma na aureta da yawa an kawo mini suka akanta na rintse idona domin cika wasiyyar da abokina ya bari na kuma yi imani da cewa babu wani kulunboto da za ta yi yayi tasiri a kaina don haka kada ki gazgata kema tunda ba ki ta'ba gani da idonki ba, ki dubi alherinta kawai idan ma tana yi wannan tsakaninta ne da Allah."
Shiru na yi na wani lokaci kafin na ce." Allah Ya kyauta amma tsakani da Allah wasiyyar nan da aka bar maka ba ta yi mana rana ba shi kuma duk cikinku ya rasa wanda zai bar wa wasiyyar auran matarsa sai kai, anya babu lauje cikin nad'i kuwa."
Ya 'bata ransa sosai Yana fad'in." Amina ba ni son abinda zai daga mini hankali a yanzu, na gaya miki maganar nan tun farkon fari wallahi tallahi babu wani dalili da zai sanya na ci amanar abokina wai da ransa na kwadaitu da matarsa kuma shi ya rubuta wasiyyar nan da hannunsa ni kuma na yi kokari cika ta domin na gaya miki ko ni na fadi na mutu zan yi farinciki ace shi ya maye gurbina a wurin iyalina dalilin aminci da sha'kuwar da take tsakaninmu."
Na ce." To na ji amma ai tun kafin ya rasu kake yabonta tare da fad'in kyawawan halayenta har cewa kake yi ta iya soyayya."
Ya dafe kansa kafin ya ce." Na fadi hakane saboda ki yi koyi da ita domin ni mutum ne mai son a kula da ni a kuma tarairayeni da soyayya. Zan gaya miki gaskiya wannan ma yana daya daga cikin dalilan da suka sanya nake yabonta saboda ba ta tsallake umarnina kuma duk abinda na nuna masa soyayya tana yin fiye da yadda na yi idan kara na ajiye bata tsallakewa ke kanki da ta fahimci ina sonki ta taya ni sonki domin ban ta'ba ganin kishinki a tare da ita ba."
Murmushi na yi na takaici na yi shiru ban ce komai.

Idan ki ka karanta ba ki biya ni hakkina ba ina bin ki bashi.

Ya rike hannuna yana fad'in." Maganar nan don Allah kada a sake tashinta matar nan tana cikin halin rai da rayuwa ni dake da duk wani makusanci a gare ta adduarmu take buk'ata, kada ki yadda zantukan mutane su rusa miki tunani da Imani, ita kuma Hajiya Aziza na raina wayonta wallahi ai Maryam sanin da nayi 'kawarta ce sosai Aminiya abokin b'arawo ai b'arawo ne Amina mai zai sanya daga zuwa kawai ta gaya miki abinda ya jima.. Ubangiji ya

hana fallasa asirin bawansa mussaman idan bawan nan ya yi tabbatacccen tuba."
Da mamaki na ce." Har yanzu dai ba zaka daina take gaskiya ka fifita karya ba ko, kai tsaye ka ki ka aminta da zantukan da suke yawo a gari akan matar nan, kai ma da bakinka ka fad'a cewa an gaya maka amma sai kame-kame kake yi kana kare ta Hajiya Aziza ai ba ta yi lefi ba tunda komai dalili yake yi.".
Ya ce." Ba wai kare ta nake yi ba Amina na ce miki Allah ne ya yi hani da cewa idan daya daga cikinku ya aikata kuskure ku yi shela a duniya mussaman idan bawan nan ya tuba babu wanda yake shiga tsakanin mahallici da bawansa."
"Ka tabbatar da cewar ta tuba?"
Da tsawa ya ce." Ke Amina maganar nan ta isa haka na ce miki wai ke wace irin yarinya ce ne, idan har ba ki nemi fitina ba ba kya jin dadi a rayuwarki ke ba za ki ta'ba ba ni nutsuwa da kwanciyar hankali ba."

Cikin dauriya na ce." Babban abinda ya daga mini hankali yadda har ka iya rufe Idonka ka gaya mata cewa Kamalu ya ta'ba yin fitina irin ta 'kuruciya a baya, sannan ka fitar da rikicin da ya faru a gidan nan har jama'a suna yamadidi da mu cewa mun had'e mata kai ni da Hauwa ba ma yin mu'amula da ita."

Ido ya tsira mini a rikice ya ce." Yanzu wanene ya kawo maganar Kamalu anan?"
Na ce." Ni ce na kawota domin na yi iyakacin bakin kokarina akan na ga na danne maganar a zuciyata na kasa abinda ya sanya ni sake gazgata cewa kai ka gaya mata a ina mutane za su samu labarin zaman da muke yi har su zage mu akan mun ware matarka tuntuni ka nuna hadin kan dake tsakanina da Hauwa baka so saboda ba mu sanya matarka a cikinmu ba har ka gaza ha'kuri ka fitar da maganar duniya."

Ya jima yana kallona cikin tashin hankali kafin ya ce."  Ni ko Hajja ban ta'ba gayawa sirrin gidana ba mahaifiyata kenan. Baban Saude shine mutumin da nake ganin zan gayawa matsalar da ta shafe ni ya ba ni shawarwari saboda na yarda da nutsuwa da adalcinsa kuma ki ji tsoron Allah Amina
Idan har za ki yi mini adalci  ki fadi gaskiya akaina kada neman fitina ya sanya ki haddasa mini ciwo, ki fadi gaskiyar abinda ki ka sani a kaina na daga da'bia na tabbatar da cewa tsayin zamana dake zaki gane abinda zan aikata da kuma wanda ba zan aikata ba mai zai sanya kawai na zaunar da Maryam na gaya mata abinda ya faru a baya me yasa zan yi haka? Uhm me yasa zan aibata Kamalu a wurin Maryam saboda soyayya ta yi mini dadi."
Ya kai karshen maganar cikin yanayi na damuwa da alhini."
Na ji hawaye sun zubo kumatuna ban goge ba na ce." To a ina ta samu labari idan ba kai ka gaya mata ba, ita kuma ta gayawa yaranta."
Ya yi d'an jim kafin ya furta." A lokacin da abin ya faru ke kan ki fa kin yi dogon rubutu a social media wato fecebook rubutun da ya zagaye kowace

kafa ta sadarwa wanda bai san akan wane dalili ki ka yi rubutun akaina ba zai je ya bibiyi ba'asi kin manta da haka? kin manta cewa Salim zai iya cin karo da labarin ke ma fa kin bada gudummuwa wurin 'kara rura wutar lamarin domin dai kin san matsayina rubutunki kuma ya janyo cecekuce da yawa, me yasa za ki d'ora mini lefi?''
Shiru na yi ina kuka domin bakin cikin abinda ya faru ne gabad'aya ya taso mini.
Ya tashi tsaye yana fad'in." Ke duk yadda mutum ya so da ya zauna lafiya dake ba za ki ba shi damar hakan ba, ba ki iya rarrashi da tarairaya ba sai neman fitina."
Ya tafi ya je ya kwanta saman gadona tare da rufe k'afafunsa da bargo. Kuka na ci na koshi yana kallona bai ce mini komai ba. Na shiga bandaki na yi wanka na fito duk idonsa biyu na shirya jikina da kayan bacci.
Abinci na zauna na ci kad'an kafin na kwashe kayan na kai kicin na dawo d'akin yana dai kwance amma bai yi baccin ba.
Gefansa na zauna ina d'an kallonsa gabad'aya ya yi sanyi yanayin damuwa ya bayyana a fuskarsa.
Ban ce komai ba na ra'ba daga gefansa na kwanta ina jin bai fi sau uku ba ya ta'ba kwana a d'akina ba.
Ya mik'a hannu ya kashe fitilar gefan gado kafin ya janyo ni jikinsa sosai ya matse ni a kirjinsa muka sauka ajiyar zuciya kusan a tare jikinsa na dan rawa na ji maganarsa a hankali cikin taushi da rarrashi Yana fad'in." Da zan iya ha'kuri dake Amina da tuni na yi, Allah Ya jarrabe ni da sonki kada ki ga haka ki nemi halaka ni don girman Allah."
Shiru na yi ban ce masa uffan ba ina jin dai yadda hannunsa keta zarya a sassan jikina. yana mika bakinsa wuyana yana sumbata cikin sar'kewar murya yake fad'in." Mu yi soyayya irin wadda na Annabi s.a.w ya koyar Amina kada mu cutar da wani sashe na jikinmu ina buk'atar kulawa a yau ta mussaman kada ki yi mini 'kwange ki marabce ni da zuciya da gangar jikinki."
Na dai yi masa shiru ban tanka ba zuwa lokacin ma na fara bin  layinsa. Ya dago fuskata yasa bakinsa yana ta sumbatar kumatuna kafin ya fara ko'karin had'a bakinmu wuri d'aya. Hannayena na sanya a tsakaninsa na janyo shi sosai muka had'e bakinmu cikin wata masifaffiyar runguma wadda take motsa duka ga'bban jiki.

Washe gari da safe kafin ya fita har da yi mini wa'kar soyayya ta Hamusu bireka tun ina daurewa har dai na gaza na dinga kyalkyala dariya ganin yadda yake ta rero wa'kar (Ashe da rai nake sonki jaruma ba da zuciyata ba, komai ruwa da iska akan ki ba za na daina kewa ba, idan na same ki.....) Na tambaye shi a ina ji ya wa'kar har ya haddace baitikan irin haka ya ce a gari ya ji shima. Kai na ci dariya sosai da ya fita na ce lallai na cinye wasan a daran jiya kenan irin wannan wa'ka haka......✍
2k complete on telegram via 0542382124...binta Umar gtbank
*07084653262*

A cikin kwanaki biyun da suka kasance na girkina mun yi abin arzi'ki sosai ni da shi ya dinga lalla'ba ni tare da ko'karin ganin wata matsala bata faru ba wadda zata janyo mana k'ananun maganganu . Washe garin ranar da girki ya bar hannuna kafin na sauko daga saman na sake tuntu'barsa maganar zuwa maiduguri ganin d'akin Fadila ya ce ai ya riga ya rantse na yi hakuri har su je su dawo daga asibitin da za su je shi da Momi tunda yanzu abinda ya sanya a gaba kenan idan ya dawo sai ya raka ni mu je maidugurin tare, shima sai ya gaishe da su Dada da sauran 'yan uwana,
Na ce amma maganar yara fa kai tsaye ya ce mini suna tare da Nabila a gidan domin ta d'an kwana biyu da zuwa wurin 'yar uwata, amma ba da ita za a yi tafiyar ba zata zauna ta kula da yaran gabad'aya har da su Salim da Adamu.
Rashin abin fad'a ya sanya ni kawai zuba masa ido, wace irin masifa ce ne wannan jama'a, shin yaushe yaranmu za su dawo hannunmu ne ni Aminatu?"
Ina zaune har ya gama kintsa jikinsa muka sauko tare babu kowa a falon Baba Tabawa ta gama aiki tun da wuri ta shige dakinta. Hauwa ba ta fito ba. Har zai fita sai ya tsaya yana kallona kafin ya ce." Ina Hauwa ne?"
Kai tsaye na ce." Ba kasan inda take ba?"
Ya zura mini ido na 'yan sakkoni kafin ya gyad'a kansa ya kama hanyar fita yana fad'in.'' idan ba ki yi tsiwa ba ai ba sunanki Amina ba."
Ya fice a gaggauce don da alama yana da wani babban uzurin da ya hana shi tsayuwa ma ya karya kummalo.
Ina juyawa da zummar shiga d'akina Hauwa ta fito cikin kayan bacci da alamar ba ta jima da tashi ba hankalinta na wurin cin abinci. Tana hamma ta furta." Wata mashahuriyar yunwa ce ta tashe ni Amina."
Na ce." Ai fa wannan abinda yake cikin naki acici za mu sanya masa Hauwa."
Dariya ta yi tana fad'in." Na dai kusa saukewa na sha ibada wallahi."
Cike da kulawa na ce." Ubangiji Allah Ya sauke ki lafiya, yanzu nan kuwa maigidan da zai fita yake tambayarki."
Ta yi sororo tana kallona. Na gyad'a kaina ina fad'in." A shawarce Hauwa tun kafin manya su ji wannan abin ku shirya tsakaninku don Allah ke ce 'kasa dashi dole ki sauke girman kan ki."
Ta ce." To so ki ke yi na je na ce masa ya yi hakuri ya janye sakin da ya yi mini Amina?"
Na ce." E, mana menene a ciki idan kin ce masa ka yi hakuri."
Ta'be bakinta ta yi ba ta ce komai ba ta nufi wurin da abin kari yake a shirye tana fad'in." Zancen ki ke so Amina."
Na bita da kallon mamaki kafin na girgiza kai na wuce d'akina da tunanin abin a raina. Da alama shi ya fara sakkowa tunda har ya tambayeta na tabbatar da cewa yanzu ya fara neman zaman lafiya a gidansa.

Ranar da za su tafi
har gida ya yi mata jagora domin ta yi mana sallama. Zamanta ke da wuya Hauwa ta yun'kura ta tashi ta shige dakinta. Hakan kuwa bai yi mata dad'i ba, amma dai ba ta ce komai ba, muka d'an ta'ba hira sama-sama kafin ya

sauko daga saman suka fita tare. Sosai na yi mata addu'a da fatan alheri ta dinga godiya da murmushin nan nata wanda duk rintsi baya ta'ba d'aukewa daga saman fuskarta.

Bayan tafiyar su da kwana ashirin da shida Hauwa ta haihu. Cikin ikon Allah ta haifi d'anta namiji kama da ubanshi har ta 'baci duk abinda ya kamaci ta yi wa kanta ta yi tunda haihuwar gida ta yi kuma lafiya lau ita da yaron da ta haifa, a matsayinta na ma'aikaciyar lafiya taimakon da muka yi mata kad'an ne. Sai bayan da muka samu nutsuwa gabad'ayanmu ni da ita tukkuna na nemi maigidan da yake koda suka tafi ba kasafai yake kiran waya ba sai dai mu had'u ta whasap to baya jurar typing sai da vedio call. Sai na ajiye masa sa'ko ta whasap din tare da hoton yaron nasan daga zarar ya hau zai gani. Ina idar da sallar la'asar na bud'e sakonshi ya shigo yana online din muka sake gaisawa na tambaye shi mai jiki ya ba ni amsa mai dadi jiki yayi kyau domin a karshen watan da muke ciki ma za su dawo domin an d'orata akan maganguna kuma alhamdulillahi an samu cigaba. Sai ya d'ora da fad'in wai na yi wa yaron hud'uba da sunan Ahmadu domin shine sunan da ya rad'a masa. Rashin abin cewa ya sanya ni yi masa shiru kawai domin tunda Hauwa ta haihu take kiran yaron da sunan mahaifinta wato Ishak, ban san kuma mai zan ce mata ba gaskiyar magana kenan.
Ganin na yi shiru ban ce komai ba ya sanya shi kiran sunana na kalle shi tunda bidiyo call ne ya furta." Ko akwai wata matsala ne domin na karanci damuwa a cikin kwayar Idonki."
Na girgiza kaina a nutse na ce." Babu matsala amma gaskiya ba zan iya gaya Hauwa ga abinda ka yanke ba, mai zai hana kai ka gaya mata naga tare kuka samar da yaron nan ku biyu mai zai sanya ni ka saka ni a tsakiya. Hauwa tunda ta haihu take kiran yaron nan da sunan babanta, to ni mai kake so na ce kuma."
Ya yi shiru yana kallona kafin daga bisani ya ce." Shikkenan zan gaya mata hukuncin dana yanke hakan ya yi ko."
Na gyada kaina ina fad'in." Ya yi shine daidai sai ku tsayar da matsaya a tsakaninku, Allah Ya raya mana shi."
Ya amsa da "Amin. Yana mai zuba mini ido."
Ni ma na zuba masa nawa idon nan na fahimci canzawar da ya yi har da wani kumatu fatar nan ta sake yin fresh duk da bidiyo call yana sanya mutum muni da duhu to shi ban ga hakan ba, kamar ba wanda ya tafi jinyya ba ya yi kama da ango wanda ya tafi yawon sha'katawa da amaryarsa.
Ajiyar zuciya na sauke yayin da nake ko'karin kawar da abinda na ji yana yun'kuro mini a game dashi na ce." Na canza kammanni ne Allah Ya taimaka ka."
Sai ya rausayar da kansa yana ce wa." Sosai kuwa, wata na gani anan asibitin da muke mai kama dake duk sanda na yi ido hud'u da ita sai hankalina ya tashi wallahi yanzu ina cikin tsananin damuwa na yi missing d'inki my love dina."
Na dan bata rai tare da cewa." Matar kuma idan tana da aure fa, kana raya abun da bai dace ba akan matar wani daidai kenan a wurinka."

Kansa ya girgiza kamar karamin yaro ya furta." Ba daidai ba ne, amma ba na tsammanin ai tana da aure budurwa ce, wallahi ba zan munafurceki ba Amina ba na iya d'auke kaina daga kanta domin yanayin hallitar jikinku daya 'yar duma-duma ce mai yawaltaccen kirji da tudun mazaunai."
Dariya maganar ta ba ni na danne ban yi ba domin ganin abin nasa yana nema ya wuce makadi da rawa na ce." To sai ka tuntubeta idan ba ta da aure ka aurota ko?"
Ya girgiza kansa yana ce wa." A'a ai ba musluma ba ce addinin hindu ce."
Na ce." To menene a ciki sai ka musuluntar da ita."
Kansa ya girgiza tare da furta." A a, abinda ya sa ki ka ji ina yi miki maganarta kamar da kuke yi da ita ne ya b'aci da gaske
idan na ganta ina shiga yanayi na buk'atuwa sosai."
Shiru na yi ban ce komai ba. Sai ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Ina nan dawowa my love za mu sha soyayya ko?"
Na kashe idona tare da fad'in." Sosai ma irin wadda kake so za mu yi."
Sai ya zuba mini idanuwansa babu kiftawa. Na kama dariya ina fad'in." Ka na ji kamar ka d'auko ni daga cikin wayar ko?"
Ya gyada kansa yana lumshe Ido. Hakan ya sake jefa ni a damuwa da sha'awa na sauke ajiyar zuciya a kasalance na furta." Ni ma na yi missing din Baba Yallabai baban soyayya."
Kafin ya ce wani abu kiran da aka yi masa a wayar ya katse video call din. Na kashe wayar tare da ajiyeta a gefe Ina sauke ajiyar zuciya gabad'aya hirar nan da muka yi ta tayar mini da hankali wani irin nake ji a jikina.
Sai gefin magriba na fito falon daga cikin d'akin Hauwa na ji kukan yaron ya tsananta da saurin gaske na shiga d'akin na same shi kwance cikin net dinshi yana ta wutsil-wutsil towel ya toshe masa hanci. Da azama na zuge net din na d'auko shi fuskarsa ta yi jazur saboda da alama ya jima yana kukan.
Na zauna gefan gadonta ina jijiigashi gabad'aya ya shid'e a tunanina tana bandaki na tashi tsaye dashi a kafad'ata na tsaya kofar band'akin ina kiran sunanta shiru bata amsa ba kuma babu motsin ruwa. Sai kawai na kutsa kaina ciki wayam babu alamunta. Da sauri na fito gabana na dan fad'uwa na tsaya ina rarraba idanuwana a d'akin ban ga alamun komai ba..
Na fita kai tsaye kicin na nufa Baba Tabawa ta kammala abinci dare tana gyara kicin din. Cikin kasala da sagewar gwiwa na furta." Baba ina Hauwa?"
Sai kawai ta tsaya tana kallona kafin daga bisani ta furta." Ba ta dakinta ne Amina?"
Na furta." Kwarai kuwa, fitowata daga d'aki kenan na ji kukan yaron nan koda na shiga d'akinta bata nan."
Ta sanya hannunta ta kar'be shi a sanyaye ta biyo bayana muka tsaya a tsakiyar falon. Ina Hauwa za ta tafi to. Ni nake tambayar zuciyata dalili tunda ta haihu ban ga alamun fitina a tattare da ita ba asalima wani babin annashuwa da farinciki ta bud'e. Baba Tabawa ta sanya babban towel ta goya yaron ni kuma na d'auko hijabina na sanya na fita can harabar gidan. Daga nesa na tsaya ina hangen securitys a bakin gate. Masa'udu ya shigo da mota ya ajiye a wurin da motocin suke ya fito daga motar ganina a tsaye ya

sanya shi da sauri ya nufo ni. Ya risina yana gaishe ni na amsa tare da fad'in." Daga ina kake domin kuwa zuciyata ta fara hasashen wani abu......✍
*2k complete a kan telegram via 0542382124...Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *2K Complete ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP 1K...0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*109*
Kai tsaye ya furta." Na kai Hajiya k'arama tasha zata bi mota zuwa bauchi don haka na ji tana fad'a a waya kafin mu isa."
Ba tare da na sake cewa komai ba na kad'a kaina na koma ciki gidan raina a masifar b'ace. Anya kuwa Hauwa tana da hankali ta haihu kwana biyu kacal saboda mugun abu ta gudu ta bar jaririn da ta sha dawainiya da wahala a kansa kafin ya zo duniya ta kuma ci kwakwa duk a kansa tare da tsallake siradi. Ga kuma d'aita irin ta haihuwa da rashin kwari a jiki, wannan ba tunani ba ne gaskiyar magana a wannan karon ba ta kyauta ba, shi jariri ina ruwansa kuma hakkinsa kad'ai ba zai bari ta samu nutsuwa ba a duk inda take.
Baba Tabawa ta dinga sallallami tana fad'in." Wannan wane irin sakarci ne Hajiya Amina, to shi wannan din da ta tafi ta bar shi ai hakkinsa ba zai bar ta, ina ruwansa da abinda ya faru."
Ban ce mata komai ba na shige na je na d'auko wayata layinta na dingi kira wayar a kashe na kira ya kai sau goma amma is switch off. Na zube saman kujera ina Kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un, wace irin masifa ce wannan ne?
Na jima cikin wannan yanayin kafin na d'auki wayata dake saman cinyata kai tsaye lambar Dr Sailuba na nemo itace tsayayyiyar likitan da take duba ni a duk lokacin da na samu ciki mussaman cikin baby Nana ta taka muhimmiyar rawa kwarai da gaske. Abu na farko da zan yi shine samarwa da yaron abinci matsalar raino wannan mai sau'ki ne. Bayani na yi mata sosai amma ban sanar da ita cewa uwar yaron ce ta ajiye shi ba.
Ba mu yi sallama da ita ba sai da ta tabbatar mini da cewa da kanta za ta shigo ta kawo mini duk abinda ya dace.
Na kashe wayar tare da zubawa Baba Tabawa idanu tana ta faman safa da marwa a katafaran falon duk domin hillatar yaron da yake ta kusurkusur da alamun kuka.
Sai da bacci ya d'auke shi tukkuna ta zo ta zauna a gefana tana fad'in." Ko a tarihi ban ta'ba ganin shashashar uwa irin Hauwa ba Hajiya Amina lallai ta gwadawa wannan yaro rashin Imani."
Shiru na yi Ina nazari kafin daga bisani na furta." Tana so ta huce fushin abinda ubansa ya yi mata shine ta dire shi ta yi tafiyarta. Abin mamaki kuma ita da mijin nata jini guda ne mamansa ta cika nono ta bawa Mamanta wace irin zuciyace wannan."

Kai tsaye ta ce." Zuciyar kafurai ce."
Muka yi shiru cikin alhini kafin ta cigaba da cewa." Ita kanta na tabbatar da cewa wallahi hankalinta ba zai ta'ba kwanciya ba ciwon jiki da ciwon nono ma ya isheta.
Murmushi na yi tare da cewa." Ciwon nono mai sau'ki ne a wurinta tunda likita ce tana da hanyoyin da zata magance abinta ciwon jiki kam zata sha ai haihuwa ba wasa ba ce."
Haka muka kasance cikin zullumi da tararrabi har Dr Sailuba ta zo ta tafi muna zaune a falon cikin wani irin yanayi na mamaki da takaici.
Ba ni da niyyar sanar da kowa wannan lamarin amma dole maigidan ya sani domin duk wanda ya sayi rariya ya san za ta zubar da ruwa, domin duk abinda yake faruwa shine sanadi me ake yi da zuciya irin tasa ta riko da ba'kar gaba, ita dashi duka kanwar ja ce shi ba'kar zuciya da gaba ita girman kai da rashin tsinkaye.
Sai da daddare tukkuna yaron ya gama kiciniyar kukansa Baba Tabawa ta goya shi ya yi bacci sannan na samu sararin bude data.
Na duba shi ta What'sapp din bai jima da sauka ba. Sallama na yi masa tare da barin datar a bud'e na ajiyar wayar na tashi na je na leka d'akin Baba Tabawa tana zagaye a d'akin bayanta goyo da yaron. Tausayinta ya kama ni haka kawai sun sanya  tsohuwa wahala lokacin da suka jiyar da junansu dadi har suka samu 'karuwa bata sani ba, yanzu kuma sun haihu sun barwa wasu da raino.
Ta juyo tana kallona a dan sanyaye na ce." Ya yi baccin ne?'
Ta gyada kanta a hankali ta furta." Ya yi da farko dana kwantar da shi shine fa ya tashi na sake mayar dashi na goya."
Na sauke ajiyar zuciya tare da fad'in." Ki yi hakuri Baba an tashe ki a tsaye."
Sai ta yi dariya tana fad'in." To menene a ciki ni na kar'bi ladan Amina duk da ban ta'ba haihuwa ba ai na iya raino an sha kawo mini yara na yaye su ki tambayi Hajiya Sahura ni ce na yaye Yasir kanin Yusura."
Da d'an murmushi na furta." Ai na ga alama duk da haka dai idan ya yi bacci sai ki kwantar da shi kema ki huta da tsayuwa."
Ta furta." Haka za a yi in sha Allahu."
Na juya na fita zuwa d'akina.
Ina d'aukar wayar na duba naga sakon shi voice note ne na buda na saurara yana gaya mini Momi ta samu sau'ki sosai ta ce tana so mu gaisa.
Ban mayar masa ta hanyar murya ba na rubuta masa a rubuce
"Hauwa ta ajiye maka jaririnka ta tafi."
Yana karantawa kuwa sai ya kira ta What'sapp din na daga.
Ya ce." Me ki ka ce?" Na ce." Hauwa ce ta tafi Bauchi ta bar jaririn a gida."
Cike da wani irin yanayi na rikita ya ce." Ta tafi Bauchi ta bar jariri bisa umarnin wa? Me yasa ba ku da hankali ne Amina?"
Da mamaki a tare da ni na ce." Ba mu da hankali kamar yaya? Ni kuma ina ruwa don na gaya maka sai hakan ya zama lefi idan na yi shiru kuma nan ma ya zama lefi."
Ya ce." Da zata ta tafi mai yasa ba ki hana ta ba, ashe ba za ki iya tsaya mini a gidana ba idan ba na nan?"

Dan murmushin takaici na yi kafin na furta." Wallahi ni kaina ban san lokacin da ta tafi ba, kuma tunda ta haihu ban ga alamun fitina a tare da ita ba, sannan da kake cewa na hana ta ni na isa? zaman idda take yi fa tunda duk cikinmu babu wanda ka gayawa ka mayar da ita don ta haihu ta ajiye maka d'anka lefi ne, tun kafin ta haihu kake da dama a hannunka ba ka yi amfani da ita ba."
A d'an raunana ya furta." Ba ki ga lefinta ba kenan Amina tare da hadin bakin ki Hauwa ta yi mini wannan wulakancin."
Na furta." Kada ka d'auki hakkina wallahi ban sani ba, bata kyauta ba ai ko babu komai ta duba yaron ta tafi dashi idan ma ba zata zauna ba."
Ya ce." Yanzu ina yaron yake?"
Kai tsaye na ce." Na aikawa da Nabila shi."
''Kin aikawa da Nabila shi?''
Ya maimaita amsar dana bashi cike da mamaki.
Na ce." Kwarai kuwa sai ta had'a gabad'aya ta ri'ke da 'yan uwansa ko ba haka ba ne tsarinka."
"Ke ba za ki iya ri'ke shi ba kafin na dawo na yanke hukunci.''
Ya fad'a cikin sanyi murya tabbacin ya ji ciwon abin."
Na ce." To ai gani na yi ba ni da nonon da zan ba shi, kuma ban iya raino ba da kula ba shiyasa na aikata mata dashi ta had'a shi ta ri'ke."
Ya furta." Kin so kema ki tozarta ni Amina, na gode bisa wannan abu da kuka hadu ku ka yi mini Allah Ya saka mini."
Bai jira jin abinda zan ce ba ya datse kiran ya ma sauka daga Whasap din gabad'aya.
Na yi kasa'ke da waya hannuna ina dariya wai Allah Ya saka masa ashe da ciwo kenan. Hauwa ta kyauta bata kyauta ba, lallai abinda ta yi ya ta'ba shi ainun ganin bakinsa ya mutu ya rasa abinda zai ce.
Kafin na kwanta sai da na sake zuwa na leka d'akin baba Tabawa yaron ya yi bacci cikin net din sa, itama ta kwanta amma ba ta yi baccin ba tukkuna na tsaya muka d'an yi maganar kad'an kafin mu yi sallama na je na yi shirin kwanciya.
Da safe ina bud'e data sakon shi ya shigo yana gaya mini jiya ya tambayi Nabila ta ce ita yaron baya hannunta. Ina muka kai masa d'ansa.
Dariya na yi kafin na rubuta masa cewa." Gidan marayu muka kai shi."
Yana dubawa kuwa ya kira bidiyo call.
Bai bari ma mun gaisa ba ya fara fadin." Kin ga ki gaya mini gaskiya don Allah ba ni son abinda zai daga mini hankali jiya ban yi baccin kirki ba Amina ban san ba ku da Imani ba sai yanzu."

Idan ki ka karanta ba ki biya ni hakkina ba ina binki bashi.

Ina kallonsa da gaske din a rikice yake yanayinsa ya nuna alamun damuwa da tashin hankali. Daki ne na mussaman shi da matar tasa don ina hangenta a can wani gado a kwance irin na marasa lafiya shi kuma yana wata kujera.
Na ce." Ba mu da imani fa ka ce?"

Ya gyad'a kansa yana fad'in." Kwarai kuwa ba ku da shi wallahi, kin ga yanzu yadda za a yi tunda ita ta gudu ta bar shi ke ki yanke abinda ki ke so na biya ki ki kula mini da shi kafin na dawo."
Na ce." A a daka bar shi a hannun Nabila zai fi alheri, idan zan kula da shi har sai na kar'bi kudi a hannunka mai ka mayar da ni."
Ya ce." Nasan ki da alheri ai, don girman Allah idan yaron nan yana wurinki ki sanar da ni hankalina zai kwanta jiya na gaya miki mun yi magana da Nabila ta ce mini ba ki kai mata shi ba."
Ganin yadda yake had'a ni da Allah ya sanya ni cewa." Yana hannunmu ni da Baba Tabawa cikin kulawa da koshin lafiya kuma tun jiya na kira Dr Sailuba ta had'a mishi duk abinda aka buk'ata."
Ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Na gode sosai my love life Allah Ya yi miki albarka.
A dan sanyaye na ce." Babu komai." Ina hangen Momin ta tashi zaune daga can wurin dake tana kallonshi shi ya juyo mata baya ya dage sai kalamai yake yi mini na dadin baki.
Na ce." Ka juya ka ga ta tashi fa."
Ya d'an juya a hankali yana fad'in." Ok jiya na ce miki tana so ku gaisa ko, amma bari mu bari zuwa yamma zan sake ta'bo ki sai ku gaisa."
Na ce." To shikkenan a ma sha Allah na ga jikin ya yi kyau Allah Ya kara sau'ki."
Ya amsa da Amin Amin mun gode giwa Allah Ya yi miki albarka." Na ce." Amin a takaice. Ni na fara datse wayar saboda ganin kamar tana buk'atar magana da shi.

To yaro dai na d'auka tunda ta tafi ta bar shi zan yi iyakar bakin kokarina. Bayan ubansa babu wanda nake jin zan gayawa ko Hajja kuwa amma tabbas nasan Hauwa rikici da gangami ta shiryawa kanta, dalili kuwa shine yadda abin nan da ta yi ya kidima shi ba zai kyaleta ba, to ma ji ma gani dai Allah Ya kyauta.
Sai bayan sallar azuhur tukkuna na samu Hauwa a waya. Ta daga hankalinta a kwance domin ban ji alamun nadama da danasani a muryarta ba.
Jikina ya mutu sosai da kyar na furta." Kina ina Hauwa?"
Kai tsaye ta ce." Ina nan Bauchi."
Na danne takaicina tare da cewa." Ashe kin shirya hakan tuntuni to hakan da ki ka yi a ganinki daidai ne ko?"
Da d'an murmushi ta ce." Shine daidai Amina, domin wa'adin zamana ya kare a gidan tunda na haihu yaro kuma ai gidan ubansa ne tunda ba dashi na zo ba, mai zai sanya na d'auko shi na kawo shi inda babu tarbiya ba Amina sunan Amadu fa ya fi sunan ubana an ce mini ubana ba komai ba ne a lokacin da na nuna shi din wani abu ne, tuntuni na gaya miki dama ba zan jure wannan rashin mutuncin ba."
Cike da takaici na furta." Amadu fa aka ce shine Mahmudu Muhammadu. Ki tuna mai wannan sunan shine wanda aka yi duniya dominsa Annabi Muhammadu S.a.w a ganina wannan abin alfahari ne a wurinki."

Ta yi murmushi tana cewa." A a ba da wannan niyyar ya sanya sunan Amadu ba. Abokinsa mai rasuwa fa shi yayi wa takwara na ce masa ina son sunan mahaifina tunda na farko ya sanya sunan mahaifinsa daga fad'in haka ya fara gaya mini magana tabbacin dama haushina yake ji to menene saura a tsakaninmu na fita daga iddarsa da dama."
Na gyada kaina ina danne abinda nake ji a raina na ce." To kina ganin Allah ba zai kama ki da hakkin yaron ba shine ina ruwansa."
Ta yi dariya tare da furta." Allah Ya yafe mini shi kuma idan rayayyene Allah Ya raya shi."
Na yi shiru domin kamar kalaman bakina sun kare da kyar na ce." Yanzu mai ki ka gayawa inna Uwani."
Da sauri ta furta." Tun daga farko a har karshe wallahi ban boye mata komai ba, Amina ai na yi hakuri na yi kuma biyayya, ke kan ki ban shure shawararki ba, na yi ta ha'kuri tsayin wattanin dana d'auka a matsayin sakakkiya mutumin nan baya kula ni kuma bai furta ya mayar da ni ba, duk wata dama ya samu bai yi magana ba yanzu kuma ai komai ya zo karshe na gaya mata komai haka zalika ma babu wanda bai sani na a family din Babanmu."
"Kenan Hajja ta ji komai?"
Na tambayata cikin zullumi.
Ta furta." Kwarai kuwa d'azu nan suka gama waya da Inna." Na yi shiru Ina nazari kafin daga bisani na furta." Hauwa idan zu'kata sun huce a daidaita don Allah kuma yaron nan da kaina zan kawo miki shi gobe in sha Allahu rabbi, ki yi hakuri don girman Allah ki kar'bi d'anki kada ki wulakantashi domin bakisan baiwar da take tare dashi ba."
"Na rantse da girman Allah a yanzu dai Amina ko kin zo da yaron nan sai dai ki koma dashi don wallahi tallahi ba zan karbe shi ba sai ubansa ya zo da k'afafunsa ya nuna nadama akan abinda ya yi mini, idan har ke za ki iya jure wulakancinsa ni kam ba zan iya ba. Ki ri'ke shi kawai na bar miki."
Bakina ne ya mutu murus na rasa abin cewa tunda har ta riga ta rantse nasan abu ne mai mutukar wahala ko na kai mata yaron ta kar'ba......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *2K ON TALGRAM WHAT'SAPP GRUOP 1k VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*110*
To wannan lamarin na su sai dai na ce Allah ya sawwa'ke har ga Allah ban so rigimar tasu ta yi tsayin da har magabatansu su shiga ba. Saboda daga shi har ita babu yaro duka sun mallaki hankalin kansu su din masu yi wasu gyara ne, duk da mas'ala ta aure akan sameta a kowane gida amma abinda yake cikin gidan nan namu sai dai mu godewa Allah daga wannan sai wannan ashe kalmar hakurin nan da manya suke nanata mana akoyaushe tana da tasiri gabad'aya sha'ani na aure a yanzu ya zama abinda ya zama domin kuwa k'alubalan da ke cikinsa ba kowace macace zata jura ba. Zawarawa sun yaiwata wad'anda mazajensu suka rasu ga 'yan mata nan birjik a gari suna

yawo idan ma kana murna ka aurar da d'anka to ka bi shi da addu'a kawai domin kuwa zamani ya zo da mata da yawa suke ganin gwara su rayu babu aura akan yin sa saboda riskar rikici da tashin hankali idan ba a yi dace ba. Abu ne a bayyane ba kowane a yanzu zamu bud'e baki mu gaya masa cewa ba ma cikin nutsuwa ya aminta ba. Dalili ana ganin Ubangiji ai ya yi mana gamnakatar da auran attajiri wanda ba mu rasa komai ba na jin dad'in duniya tabbas ba mu rasa komai na jin dadi ba amma mun rasa kwanciyar hankali domin kuwa idan ana murna an kashe wannan wutar sai ya sake kunno wata da kansa.
Kwanaki biyu ba ni ganinsa a online hankali ya tashi domin tunda suka tafi tsayin sati uku kullum sai mun yi magana. Na shiga  damuwa sosai na kuma kasance cikin duba wayata a akai-akai. Misalin goma da rabi na yi shirin kwanciya don ban jima da fitowa daga d'akin Baba Tabawa ba na d'auki wayata na duba sakon  voice note din shi ya shigo na bud'e ina saurara yana gaya mini suna kan hanyar dawowa gobe domin sun gama shiri kuma alhamdulillahi ta ji sau'ki."
Jin haka ya sanya hankalina kwanciya domin tsakani da Allah kwana biyun nan na yi sune cikin fargaba da tunanin halin da suke ciki ko kuma na ce yake  ciki tunda ta hanyar wayar ne kawai muke magana.
Washe gari da wuri kuwa na kira yarinyar nan da ta yi mini 'kunshi ta zo ta zana mini baki da jaa kafafu da hannayena. Ya yi kyau ainun. Na ce da Baba Tabawa ta shirya masa towon somovita ayi miyar kuka domin duk cikin kayan kad'i ya fi sonta.
Tare muka shiga kicin na taimaka mata tana goye da yaron a bayanta yana bacci muna d'an ta'ba hirar  rashin lafiyar Momin har muka kammala tsaf towo semo da farfensun kayan ciki tunda shi ma yana daya daga cikin abinda yake so domin shi kam ya fi kauri ga abincin gida. Lemo kam ba kowanne yake sha ba ya ma fi jin dadin zob'on da Baba Tabawa take yi masa mai cike da kamshin citta da kaninfari.
Na riga ta fitowa daga kicin din wanka na yi a gurguje na d'aura alwala tunda daf ake da kiran sallar magriba na shirya jikina a cikin atamfa java kalar sararin samaniya mai d'auke da adon zaiba da stones a tare fittedgwon ce ta d'an kama ni amma ba sosai ba. Yanzu ina iya sanya matsatstsun kaya dalilin maganin tumbin da na yi amfani da shi wanda ya narkar mini da mugun tumbin da ya yi mini zuguda a ciki. 08089965176 wurin GARKUWAR MATA na sayi maganin yana da kyau sosai kuma harbel ne ba shi da side effect.
Ban yi cikakkiyar kwalliya ba domin can dama ban fiye fenta fuskata ba na dai shafa hoda tare da sanya kwalli na sanya jan janbaki a le'bena. Na gyara gashin kaina sosai kafin na daura d'ankwalin daidai da zamani.
Ni ce har da had'a kankana da zumar mata ta goron tula itama dai duka order ce daga wurin GARKUWAR MATA na hada da madara na cika kofi na shanye wannan hadin idan na yi shi yana bala'in saukar mini da ni'ima sosai gefe guda kuma ga ruwan kaninfarin da nake yaiwata sha shiyasa kusan koyaushe a jike nake don ba ni da matsalar bushewa balle matsi da koyaushe idan wata mu'amula za ta kasance sai ya yi kiki-kaka kafin ya samu damar ratsa jikina.

Idan ki ka karanta ba ki biya ni hakkina ba ina bin ki bashi.

Sai wajan takwas da rabi ya kira ni a waya yana gaya mini suna airport saukarsu kenan. Cike da kulawa na ce." To, shikkenan Allah Ya kawo ku gida lafiya."
Ya amsa da kulawa kafin ya datse kiran. Na ajiye wayata ni ma na fita falon shiru Baba na dakinta.
Zamana a falon da kamar minti goma  ta fito har yanzu yaron yana goye a bayanta na ce." Wai Baba har sallah ma da yaron nan ki ke yi a goye?"
Tana ko'karin zama kusa da ni take fad'in." Wataran ba, amma dai idan na ga baccinsa ya yi nisa ina sauke shi sai dai fa kafin na idar da sallar ya tashi, ai ya tsani kwanciya sai dai goyo."
Ina dariya na ce." Dama ai duk abinda aka sabawa da yaro shikkenan sai ya tasirantu da shi ki dinga kwantar da shi ko zai saba."
Ta furta." Ai rik'on hannu ga yaro irin wannan shine matsala Hajiya amma goyo daidai kenan, kuma idan dare ya yi sosai na kwantar da shi baccin mu muke sosai sai da asuba yake farkawa.
 Aikuwa kamar yana ji sai ya fara motsi ta ce." Af kin ji shi ko? shi fa baya so a goya shi a zauna zai kama tsalla ihu."
Na ce."Sakko shi mu gaisa." Ta kwanto shi daga bayanta tsaf dashi a cikin kayan sanyi masu d'umi yana ta k'amshi ni kaina sheda ce yaron yana samun kulawa wurin Baba Tabawa tamkar yana rayuwa a hannun uwarshi. Na kar'be shi Ina d'an jijjigashi da fad'in." Yau za ka ga babanka yaro."
Ta mike tare da fad'in."Bari na d'auko masa abincinsa." Ta nufi dakinta da saurin gaske.
A kafadata na sanya shi ina d'an jijjigashi maigidan ya shigo tare da Sukairaju a bayanshi. Yana cikin suit ya zanzare sosai ya yi kyau da kayan dukda bai fiye tu'ammuli da su ba amma duk ranar da ya sanya irinsu ni kaina yana burge ni. Farin gilashinsa na ka'ida yana sakaye da idanuwansa na mike tsaye da yaron a kafadata yayin da shi kuma ya juya yana kar'bar yar wasu takardu daga hannun Sukairajun ya ba shi umarnin tafiya.
Baba Tabawa ta fito hannunta ri'ke da fida cike da madara ta washe bakinta tana fad'in." Sannu da zuwa  sannu da hanya ranka ya dad'e fatan an dawo lafiya?"
Ya amsa da kulawa. yana fad'in." Lafiya lau Baba mun same ku lafiya? Ya kokari kuma na gode sosai Allah Ya saka da miki da alheri."
Ta d'an sunkuyar da kanta tana fad'in ." Babu komai wallahi, ai babu buk'atar godiya Alhaji."
Bai ce komai ba ya dubi wurin da nake tsaye na saki fuskata sosai Ina fad'in." Barka da zuwa."
"Barkanmu dai Allah Ya taimake ki." Ya fadi hakan cikin sigar tsokana kafin ya fara ko'karin haurawa samansa. Na kar'bi fidar yaron dake hannun Baba Tabawa na bi bayansa.

Na same shi yana ta ko'karin cire safar dake kafafunshi. Ya dago yana kallona kafin ya furta." Amarya."
Ban ce komai ba na zauna gefanshi  ya miko mini hannu yana fad'in. Ba ni abokina mu gaisa."
Na mika masa yaron ya kar'ba ya tsira masa ido sosai kafin ya gyad'a kansa yana fad'in." Wallahi Amina Hauwa ba ta da imani ko kad'an."
Na yi shiru Ina kallonsa ya sanya bakinsa a kunnan yaron hagu da dama ya jima a haka kafin ya sake duban fuskarsa ya ce." Amadu shine sunanka, ina ro'kon wanda ya ba ni kai ya rayaka tafarkin addinin Islama, ya raya mini ku bakidaya."
Na amsa da "Amin Ya Allah."
Ya miko mini shi yana fad'in." Ina can hankalina yana nan Amina Amma alhamdulillahi na ji dadin ganinku cikin nutsuwa da kwanciyar hankali lallai Allah Ya azurtani da matar rufin asiri kuma Mar'atussaliha, na godewa Allah na kuma gode mini bisa abinda ki ka yi mini."
Maganganunsa sun sanya mini mutuwar jiki,  na dube shi karon farko da na ji tausayinsa ya tsirga mini. Na janye idona daga kansa can kasan zuciyata ina ji tana fad'in cewa ba matausaya ba ne ba fa.
Na danne dai tare da furta." Ya mai jikin, koda yake alamar karfi tana ga mai 'kiba wai ka gan ka kuwa yadda ka wani zanzare wai kuma jinyya ka tafi gaskiya ka fi kama da wanda ya tafi yawon sha'katawa."
A sakarce ya kalleni yana ko'karin cire gilashin idonsa ya ce." Wane sha'katawa bayan babu babbar sha'katawata a kusa da ni, ai ke ce karshen sha'katawa Amina."
Murmushi na yi ina kallonsa. Ya ce "Da gaske nake gaya miki kece sha'katawata, na ga kin yi kama da amarya yau tunda na kalle ki nake ganin kamar sabuwar amarya na yi."
A gajarce na ce." Wani Abu ya canza a jikina ne?"
Ya furta." Kwarai kuwa ga lalle an ranga'da mini, an yi mini kwalliya na yaba sosai sai a fadi nawa ne kudin lallan na biya."
Na furta." Ai ba zaka iya biya ba."
"Me yasa?" Ya fad'a yana ko'karin mi'kewa tsaye.''
Ban ce komai ba ni ma na tashi ina fad'in." Bari na mik'a yaron nan wurin Baba ta goyo shi bacci zai koma."
Ya furta." Ya yi, zan yi wanka yanzu na sauko cin abinci  sai mu sake gaisawa ko."
Na ce." To shikkenan sai ka sauko." Hanyar fita na nufa ina d'an jijjigashi yana ta motsin kuka.
A falon ya same ni muka nufi wurin cin abincin tare yana fad'in." Hauwa ta kai k'arata wurin Hajja Amina, don Allah tsakanin ni da ita wanene mai gaskiya."
Na gyara masa kujera ya zauna yana ta kallona.
Ban tanka masa ba  wai don ba ni da abin fad'a kawai maganar ce ta ishe ni haka, na ma daina sanya musu baki abinda ya shafe su ne wannan tunda shi har yanzu gani yake yi yafi ta gaskiya.

Duk yadda ya so da mu yi maganar Hauwa akan abinda ta yi ban biye masa ba, ya gaji da takalo maganar ya bari ya shiga wata ina d'an taya shi kafin a kira wayarsa. Momi ce ban san me ta gaya masa ba na ji dai yana fad'in." Subahanallahi, bari gani nan zuwa kada ki sake tashi tunda jiri na dibanki bari na zo yanzu."
Ya kashe wayar yana kallona ni ma shi din nake kallo da 'yar damuwa yake fad'in." Bari na sake dubo mai jiki na dawo Amina." A tak'aice na ce." A ce ina yi mata sannu.
Ya mike ba tare da ya kwashi wayoyinsa ba ya nufi hanyar fita yana fad'in." Yanzu zan dawo in sha Allahu."
Ban ce masa komai ba illa ido da na bi shi da shi har ya fice, ina d'an mamaki jiri kuma? Allah dai ya kawo mata sau'ki shine abinda za a ce.
Dama kusan tare muka ci abincin don haka ko minti biyar ban kara a wurin ba ni ma na tashi tare da diban wayoyinsa da ya bari na
shige d'aki wanka na sake yi na shirya da kayan bacci na zauna jiran sa.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*
*2K Complete a TALGRAM WHAT'S APP GRUOP 1K VIA 0542382124.... BINTA UMAR GTBANK.*
*V-VIP AREWA PEN*
*07084653262*
*111*
Wayata na d'auka ina dubawa amma hankalina gabad'aya yana wani wuri. A k'alla yanzu da fitarsa kimanin minti talatin kenan, a ganina idan ba wata gagarimar matsalar ba ce ya ci ace ya dawo kuma idan kuma ba acan din zai kwana ba. Zuciyata ta dinga yi mini sake-sake abubuwa da yawa ina dojewa ba ni so na aminta da sashenta ya zamana kuma ba hakan ba ne, uzuri akan ciwo abu ne mai kyau wanda hakan yake da tabbacin kai ma ba ka wuce a jarrabe ka ba. Amma tabbas zai dawo komai dare tunda duka ga wayoyinsa a hannuna.
Sahura na ga ta turo mini voice note na shiga da sauri na kunna ina saurara. Ni sai abin ma ya ba ni dariya wallahi.. Cikin jajantawa kanta da alhini take gaya mini wai Idiris an yi musu rabon gado wata tsohuwar gonar mahaifinsu aka gano a wani k'auye shekarun kusan talatin da biyu da ya sayi wurin ya jefar abinka da mutanan da tunda ya sayi wurin babu wanda ya ta'ba d'auka a cikin manyan yaransa ya nunawa ko 'yan uwansa ba su sani ba tun a wancan lokacin ya kai takardun wani tsohon banki da ya daina aiki a yanzu da yake dukiyar ta halak ce bincike dai har mahukunta suka tabbatar da gonar mahaifinsu ce  tunda da sunansa a rubuce a takardun da aka binkito takardun gonar a bankin Yanzu dai tana gaya mini an sayar da gonar miliyar sittin da biyar Idiris ya samu miliyan takwas shine wai ta ga alamar wai yana neman aure.
Na ci dariyata na k'oshi cikin zuciyata ina fad'in." Idan ban da tarangahuma ta da namiji fisabilillahi nawa miliyar takawas take da har za a rakito aure a kanta. Matsalar Malam bahaushe kenan daga zarar ya dan samu fargaba ko yaya ne sai ya ce aure zai kara.  A tunanina wannan dama ce da idiris ya samu da zai juya kudin domin dogaro da kansa. Ba a ce masa kada ya yi aure ba amma ya bari ya tsaya sosai da k'afafunsa tunda zahirin gaskiya Sahura tana kokari sosai kusan ita dashi rabi da rabi suke yi kan harkar karatun yaran ma ta fi shi kokari sosai da sosai ni kaina duk wata na kan tura mata abinda ya sawwaka tunda nasan tana da d'awainiya sosai. Wannan dalilin ne fa ya sanya wasu matan cire tausayi da imani akan mazajensu domin wallahi duk namijin da ka nunawa soyayya daga karshe yana samun dama zai yi kokarin jefa ka a rana.

Ganin ban bata amsa ba sai kawai ta kira na dubi agogo goma da ashirin da biyar na dare. Lallai abin yana damunta tunda ta gaza ha'kurin bari gari ya waye
Na daga ina fad'in." Sahura." Ta ce." Shine don wulakanci na turo miki sa'ko kin bade kin saurara kimanin minti goma ina ganinki a online din amma ki gagara ba ni amsa." Muryarta na d'an rawa ta kai k'arshen maganar. Ta d'an ba ni tausayi na danne dariya da nake so na yi na ce." Wallahi na saurara Sahura kaina ne kawai ya daure shiyasa ki ka ji na yi shiru mamaki ne ya ishe ni, in banda abin Idirs nawa miliyan takwas take da zai rakito aure maimakon ya juya kudin su ninku ba mu hana shi ba amma ai sai ya bari mu murmure tukkuna."
Ta furta." Wallahi da ni yake zancen Amina muddin ya ce zai yi aure a irin wannan yanayin sai dai ya sake ni domin ba zan iya zama da butulu ba."
Na ce." Ki saurare ni Sahura, ki bi komai a hankali dan Allah, kin san yanzu idonsa a rufe yake yana ganinsa da 'yan canji zai iya aikata komai. Kada fushi ya sanya ki zo kina nadama daga baya, ki yi hakuri ki bi a sannu ba ni son wata matsala ta faru dake."
Sai kawai ta fashe da kuka tana fad'in." Wallahi Amina ban ta'ba tsammanin Idiris zai mini haka ba, ki duba ki ga fa irin wahalar da nasha da yawon haya da ba don kin ba ni wannan gidan ba da tuni fa muna can zaune a wannan tsukakken gidan da masu shi suke yi mana wulakancin duk lokacin da suka zo kar'bar kudinsu. Kin dai sani ke kanki kin sha cika mana kudi idan lokacin biya ya yi. Yanzu yana ganin bashi da matsalar biyar kudin haya. An aurar da Yusura kuma ina d'aukar albashi tare da samun kayan abinci sa'i da lokaci a wurin aiki shine ya sakar mini wahalar gida ta sauran yaran da ya samu kudinsa bai yi tunanin komai ba sai na aure yanzu don Allah Amina idiris ya yi mini adalci."

Na ce." Bai yi ba wallahi, kuma ya yi butulci, ai shine na ce miki ba mu hana shi ya kara aure ba amma ya bari ya tsaya da k'afafunsa sosai yanzu ba lokacin da zai rakito wata ba ne. Amma kin san yawanci tunaninsu daban ne da namu kuma idan idon su ya rufe akan mace suna aikata komai a yanzu Sahura ba fata nake yi ba don Idiris ya rabu dake ba wani abin ba ne wallahi tunda baya hankalinsa."
Cikin dusashewar murya ta ce." Na gaya miki wallahi duk ranar da ya daura aure da wata to ni kuma na gama zama da shi har abada kuwa."
Bata bari na yi magana ba ta datse waya. Na yi sororo da tawa a hannu Ina mamakin al'amarin. Gaskiya Idiris bai kyauta mana ba wallahi.

Ina binki bashi domin littafin nan na kudi ne.

"Wallahi jiri ne ya d'ebe ta ta fad'i, Allah ma yasa ina d'akin da ban san abinda zai faru ba." Nabila ce take yin wannan maganar yayin da take zaune kusa da 'yar uwarta dake kwance a sambal a gado sai kace matacciya.
Ya ce." Dama ai kamata ya yi ki kasance tare da ita a koyaushe saboda jikin nata babu kwari har yanzu, sai kin kula sosai." Ya kai karshen maganar yana

duban dirowar da take gefan gadon da Momin take kwance wata madaidaiciyar jarka ce cike da rubutu da kofin gilas a ajiye.
Ya dubi Nabilan yana fad'in." Ta ci abinci?" Ta ce." Yanzu dai zan kawo mata?" Ta mike da sauri tare da kama hanyar fita.
Ya zauna kusa da ita a hankali ya kira sunanta "Maryam." Ta bude idonta tana ko'karin tashi zaune ya sanya hannu ya dago kafadunta ta tashi." Me yake damunki yanzu?"
"Ba ni jin komai sai jirin fa, daga zarar na mike zan ji hajijiya baya ga haka kuwa sai dai nace alhamdulillahi."
Ya gyad'a kansa cikin kulawa ya furta." Za ki daina ji in sha Allahu daga zarar kin ci abinci kin sha magani yanzu, amma menene a wannan a gefanki."
Ta dubi wurin da yake kallo a hankali ta ce." Sanyawa na yi aka rubuce mini al'kur'ani mai girma. Ya d'an jima yana dubanta kafin ya ce." Hakan yana da kyau, kina ji ko dole fa sai kin rage yawan tunani da damuwa, ba ke kad'ai ce ke d'auke da wannan cutar ba kuna da yawa ko a asibitin ma ai kin ga wad'anda suka fi ki jin jiki, cuta ba mutuwa ba ce za ki samu sau'ki in sha Allahu, ki dinga sanya hakan a ranki."
Sai ta sanya kuka tana fad'in. Anya kuwa, ga ni nake yi mutuwa zan yi wallahi, ba fa na jin dad'in duniyar gabad'aya, ciwon nan shi zai kai ni."
Ya ce." A a, mutane nawa ne suka yi jinyya mai tsanani kuma suka tashi ki daina sanya damuwar hakan a ranki za ki ji sau'ki in sha Allahu."
Ta dinga share hawaye tana girgiza kanta har Nabila ta shigo da plate din abinci madaidaici ya kar'ba ita kuma ta juya ta fita. Kusa da ita ya matsa sosai da kansa ya bata abincin da maganganunta ta sha. Ya sanyata a jikinsa sosai yana rarrashinta cikin tausasawa kamar yadda ake yi wa mai ciwo. Kusan sha d'aya da arba'in sha biyu saura kenan ta yi bacci ya fito Nabila na falon tana kallo ya ce ta shiga su kwana tare. Sallama ya yi mata a gurguje ya fita.
Cikin baccin da ya kwashe ni na ji motsin shigowarsa d'akina. Na bude ido ina kallonsa yana zama gefana kamshin turare biyu ya gauraye hancina k'amshinsa daban ne kuma ya zauna a jikinsa tuntuni duka kayansa k'amshin suke yi yanzu hancina na shako mini wani kamshin na daban.
Na tashi zaune ina d'an dubansa na dubi agogo sha biyu saura minti goma sha biyar ya samu kimanin awa uku babu wani abu a can.
Na ce." Ashe za ka dawo?" Ya gyad'a kansa yana fad'in." E, me zai sanya ni na kwana bayan ga amaryata tana jira ko ba ki yi kewa ta ba?"
Ya fad'a yana d'an matsowa kusa da ni. Sai na ji kawai haushinsa ya kama ni, na tsani munafurci wallahi ko bai fad'a mini ba ya rungume matar nan a jikinsa tunda ga k'amshin turaranta nan a jikinsa.
Na ce." Aikuwa da ka sani ka kwanta a can kawai dubi agogo fa ga gani."
Ya rike hannuna yana murzawa ya ce." Kada mu yi wata hatsaniya dake a wannan daran Amina, ki ba ni hadin kai da k'warin gwiwa don Allah kada kishi ya sanya ki zobe lada da albarkar da nake ta shi miki tunda na dawo kike faranta mini rai, ina ta murna Allah ya amshi addu'ata a kanki, ki ru'banya ladanki kafin gari ya waye."

Baki na zum'bura na ce." Me ka ji na fada yanzu, cewa na yi fa da ka sani ka yi kwanciyarka a can shine ya zama lefi bata fa da lafiya."
Ya girgiza kansa yana fad'in." Ba ni da wani dalili da zan kwana a can, ai ta ji sau'ki kuma kwana na nawa a tare da ita,  ai kina da hakki a kaina ni ma ina dashi a kanki kamata ya yi mu raya wannan daran ya zama ma mussaman a gare mu har ya fi na ranar amarcinmu daraja."
Shiru na yi ban ce komai ba ya d'an shafa dokin wuyana yana fad'in." D'azu dana shigo na gan ki rungume da yaron nan a kafadarki sai dana na ro'ki Allah subahanahu-wata'ala da ya ba ni namijin ko'karin samar da makamacinsa a daran yau, za ki ba ni hadin kai ko?"
Ya fad'a hucin numfashinsa na sauka a jikina.
Na kalle shi na ga ya wani saki gabad'aya kansa a langa'be ido daya a kanne. Cikin zuciyata na ce." Yaudara da iya kalamai sai ka ce goggagen d'an bariki.
Ya had'e hannunmu waje daya yana sakin ajiyar zuciya tare da d'an sake shigowa jikina. Ya kamo daya hannun na yana duba lallan yasa bakinsa ya sumbuta yana fad'in." Ko wannan da ki ka yi mini na ji dad'i har na ce Allah Ya shi albarka abinda za a ru'banya miki lada ne. Yanzu za ki cika she ladanki ina so ki nuna mini kwanzonki a wannan daran mai albarka."
Na dube shi duk ya kanainayeni. Na ce." Wane k'wazo zan nuna kuma?"
"Ya dago da sauri yana fad'in." Ki cinye ni a wasan gabad'aya hajiyata."
"Umm" Kawai na iya cewa jikina duka ya shika. A hankali ya mik'a hannunsa ya kashe fitilar gefan gadon da ta d'an haske d'akin. Sai ya yi duhu sosai. Ya rike ni da kyau tare da d'an tura ni na kwanta ya yi mini rumfa shikkenan daga lokacin ni ma na kwarkwace muka zama kamar tuburarrun mahaukata.

Da safe da wayar Hajja ya karya. Ga yanayin yadda yake amsa mata magana ya sanya mini kasala. Suna gamawa ya dube ni yana fad'in." Zan je kano yanzu Amina Amma ina sha Allah zan dawo yau idan kuma wani dalili ya sanya ni kwana zan kira waya na sanar dake in sha Allahu."
Na ce." To shikkenan." Na yi shiru ina kallonsa yana kimtsawa. Na dai kasa daurewa da nace ba zan sake sanya musu baki ba, amma na gaza ha'kuri na ce." Ka ga abinda nake ta guje muku kai da Hauwa ko?"
Ya dube ni yayin da yake sanya links a hannun rigar da take jikinsa ya ce." Ai dole dama za a zo wannan ga'bar na sani, kada ki damu ni babu abinda zai faru sai alheri ni dama ai ban ce ina sonta ba, sune suka dage za kuma ta san ni ta yi wa wannan wulakancin ai."
Na ce." Kenan a ganinka itace mai lefi kafi ta gaskiya, ko da suka dage suna son auranka ka fad'i tsakaninka da Allah da annabi cewa kai ma baka sonta."
Kai tsaye ya furta." Wallahi Samira nake so ba Hauwa ba Amina, ai na gaya miki tuntuni Samira da ita na fara soyayya nasan menene so, Allah Ya k'addara ba mu zauna ba ta rasu. Hauwa kam ba ni yi mata soyayya fitacciya gaskiyar magana"
Na ce." To mai yasa ba zaka maye gurbin soyayyar da kake yi wa Samira zuwa ga 'yar uwarta ba, ka ji tsoron Allah wallahi yanzu da bakinka kake

furtawa baka sonta. Amma mai yasa kake rayuwar aure da ita har ku haihu, menene bambacin Samirar da Hauwa tunda duka uwa daya Uba daya suke."
Ya girgiza kansa yana fad'in." Da bambamci Amina, babu dalilin da zai sanya ni maye gurbin son da nake yi wa Samira akan Hauwa, me yasa lokacin da ta rasu ta'ki maye gurbin 'yar uwarta, na fa san komai Amina, don haka ba ki da ruwa akan wannan abinda yake faruwa tsakaninmu. Ba a yi macan da za ta yi mini wannan iskacin ta kwana lafiya ba."
Na ce." To ai zumuncin da yake tsakaninku za ka duba."
Ya furta." Ita ta duba zumuncin ne?"
Na yi shiru ina kallonsa. Ya girgiza kansa kafin ya bud'e ma'adanar da yake ajiye gilasansa ya d'auko daya ya sanya kafin ya kwashi wayoyinsa ya zuba a aljihu. Ya dube ni sai kuma ya kama hanyar zai fita na bi bayansa ina fad'in." Za ka tsaya ka yi breakfast ko?"
Ya ce." A a yanzu wurin Momi zan shiga mu gaisa na wuce kawai zan ci abinci a can gidan Hajja in sha Allahu."
Muka sauko a tare ina fad'in." Shikkenan to don Allah a ce ina gaishe da Hajja da kyau tare da su Kamalu." Ya furta." Za su ji, zan gaya musu sa'konki in sha Allahu sai na dawo." Ya fice da saurin gaske.  Na juya na shiga d'akina jikina duk a mace. Ubangiji Allah Ya sa mu ji alheri.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘
*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai

ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

"Yanzu don Allah Hajja abinda Hauwa ta yi shine zumunci? nasan duk wannan fad'an da ki ke yi akan hakan ba zai wuce ace kina gudun lalacewar zumunci ba. Amma ki yi nazari akan wannan abinda Hauwa ta yi Hajja ko mahaukaciya fa ta san d'anta ki ga yadda ake yi musu ciki akan titi A
Amma su haihu a yi ta dambarwa da su wurin 'karbar jaririn daga hannunsu. Sannan kin ga yadda dabbobi idan sun haihu suke tattalin abinda suke haifa ai ko babu dangantaka ta jini a tsakaninmu da yarinyar bai kamata ta yi mana haka ba. Wannan wulakanci ne da rashin mutunci da kuma rashin tarbiya."
Hajiya Saratu ce take wannan maganar cikin yanayi na damuwa da bakincikin abinda yake faruwa.
Hajja ta d'an gyara zamanta tana fad'in." To tunda gashi nan a zaune sai mu ji menene dalili saboda ai k'arfe d'aya baya amo! ba wai ina goyuwa da bayan Hauwa akan abinda ta yi ba, ban ji dad'i ba kuma bata kyauta ba amma wata'kila duk ta yi hakan ne domin huce fushin abinda ya aikata mata. Ai ya nuna mata iyakarta ni ma kuma ya nuna mini ba ni da wani muhimmanci dangane da rayuwarsa tunda har zai iya yanke irin wannan hukuncin ba tare da ya nemi shawarata ba. A ganina kome Hauwa ta yi masa ta ci albarkacin jini da dangantaka ko."
Ta girgiza kanta tana cewa." Hajja Hauwa fa bata da kunya ba wai ina 'kin ta ba ne a a halayenta munana sun rinjayi kyawawan domin duk mai zuciyar imani da tausayi ba zai aikata abinda ta yi ba a yanzu kamar yadda na gaya miki ko daga waje Tajo ya auro Hauwa ba mu cancanci wannan iskancin ba."
Sai ta dube shi tana fad'in." Ka na jin mu baka ce komai ba, wai shin mai ya yi zafi ne tsakaninka da Hauwa da har ka saketa ko kana so ka nuna mini cewa ni ban isa ba ko kuma na ce ka d'auki hanyar lalata zumuncin da yake tsakanina da 'yar uwata da ta rage mini a duniya."
Ya ce." Hajja a yi hakuri amma ina ganin zan ha'kura da Hauwa kawai domin wallahi ban da tayar mini da rikici babu abinda take yi a gida."
Ta ce." Akan wane dalili shine abinda na tambayeka, kai yanzu baka ji kunya da nauyin gaya mini hakan ba da wane ido zan kalli Uwani.''

Ya yi shiru bai ce komai ba. Sai ta cigaba da fad'in." Ka gaya mini mai ya had'a ku da har ta yi wannan fushin ta ajiye jariri d'anyar haihuwa ta gudu, duk abinda za ka ga uwa ta aikata haka ba k'aramin abu ba ne ."
Cike da b'acin rai ya shiga warware mata duka matsaltsalun da suka dinga faruwa wasu ta san da faruwarsu wasu kuma bata sani ba mussaman akan rikicinta da Maryam da kanwarta duk ya gaya mata abinda ta dinga yi har sakin ya ratsa. Ta ce." To ai kai ma kana da lefi me yasa za ka raba su da yaransu hakan bai isheka ba ka had'a da duka da cin mutunci don haka ta gayawa uwarta ni ma ta gaya mini shin jaka ce ita da zaka dinga dukanta ko ka manta cewa diyar wani ce itama, kana so ka aurar da yaranka a dinga dukansu."
Ya ce." Wallahi Hajja sau daya na mare ta, amma ni ba ni dukan iyalinsa sharri ne kawai irin nata."
Ta ce." To marin ma kada a sake yin sa ban yarda ba, dukansu amana ne aka bamu bakidaya Hauwa ko ba ta ci darajar komai ba sai ta ci albarkacin zumunci da haihuwa ai ta zama kai ka zama ita haihuwa uku ba wasa ba ce."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." In sha Allahu ba za a sake ba. Falon ya d'auki shiru na wani lokaci kafin ta ce." Menene matsayin auranta a yanzu? Ya furta." Tuntuni na mayar da ita ai tun kafin ta haihu har yanzu tana nan a matsayin matata."
Ta sauke ajiyar zuciya tana fad'in." Alhamdulillahi yanzu ka je can bauchi wurin Uwani ka basu hakuri don ta fusata sosai har suna fad'in ka aiko musu da takarda domin su ajiye sheda."
Ya ce." To yadda ki ka ce haka za a yi in sha Allahu."
Tare da 'yar uwarsa Hajiya saratu suka shirya tafiya Bauchin da wajan la'asar bayan sun yi sallah tafiyar mota za su yi suna fitowa harabar gidan Hajja Yusi ya shigo akan sabon machine wanda Hamusu ya saya masa domin shige da fice zuwa makaranta da kasuwa tunda sun bud'e sabon shagon sayar da takalma na mata da maza a kasuwar kwari to Yusin ke kula da shagon shi da Saminu.

Cike da kwarin gwiwa ya je ya kafe babur din shi kuma Baban sai dariya yake yi ya zuba hannuwansa duka biyun cikin aljihun tazarcen dake cikinsa. Gabad'aya hankalinsa yana kan yaron fuskarsa kamar gonar audiga. Ya 'karaso wurin da suke tsaye da sassarafa sai suka rungume juna. Ya d'an dinga dukan kafadarsa yana fad'in." Abokina." Shi ma yana abokina?"
Suka cika juna amma hannunsu a hade yake ya risina yana fad'in." Baba barka da yamma yaushe ka zo ne?"
Ya dafa kafadarsa yana fad'in." Ban ji ma da zuwa ba, ni ma ina zuwa na tambayi Hajja tace mini ka fita tun safe mutumin ya zama d'an kasuwa."
Yasa dariya yana cewa." Wallahi ai da na san da zuwanka da sai na zauna domin mu gaisa sosai."
Ya ce." Idan kana so mu gaisa sosai ka zo abuja idan ka d'an yi free tunda nasan kana karatu ga kasuwa ko ta hana ka zuwa ne?"

Ya yi shiru yana murmushi kafin ya juya gefan da Hajiya saratu take tsaye tana ta dariya ganin yadda suke cafkewa dama tuntuni akwai wannan sha'kuwar mai karfi a tsakaninsu.
Ya d'an risina yana gaisheta ta amsa tana dariya kafin ta wuce wajan motar da Sukairaju yake tsaye yana jiran zuwansu ya bud'e mata gidan baya ta shiga ta zauna.

Ya ce." Yanzu Bauchi muka nufa amma ina so ka zo abuja kamar yadda na gaya maka duk lokacin da baka da wani uzuri ka duba Momi bata da lafiya, ta kwanta a asibiti jiya muka dawo gida. Amma alhamdulillahi ta ji sau'ki akwai buk'atar ka zo ka dubata ko?"
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Zan zo in sha Allahu Baba, mun yi magana da Adam kwanciyarta ta farko asibiti shi ya kira ni ma yake gaya mini ban samu zuwa ba. Ya yi fushi bai gaya mini ba yanzu, in sha Allahu idan Kamalu ya dawo da daddare zan gaya masa."
Ya ce." Hakan yana da kyau, amma baka ba ni amsar dana tambayeka ba mamanka ce ta hana ku ziyartarmu."
Ya ce." Ko daya wallahi Baba, ba ita ba ce kawai dai tunda muka dawo nan din ne ba mu samu zama ba shine kawai dalili amma idan ya dawo zan gaya masa zan kuma sanar da Baba Hamusu."
Ya ce." To madallah aboki Allah Ya ba da sa'a, Allah Ya sa ina gari lokacin da kuka shirya zuwan."
Ya amsa da "Amin Baba."
Wajan motar suka nufa a tare Sukairaju ya d'an matsa da sauri kafin ya bud'e masa motar Yusi ya yi saurin riga shi. Ya shiga ya zauna kusa da 'yar uwarsa da bismillahi yana fad'in." A gaishe mini da Kamalun idan ya dawo a gaya masa sa'kon Mamanku cewa tana gaisheku gabad'aya."
Cike da ladabi ya ce." In sha Allahu zan sanar dashi Allah Ya tsare Baba."
Ya d'aga masa hannu Yana amsawa da "Amin."
Koda suka sauka a garin bauchi Hajiya Saratu ce kadai ta yada zango a gidansu Hauwa domin shi kam tun a mota ya ce tunda dare ya yi Sukairaju ya kai shi hotel din da ya saba sauka idan ya shiga garin suka kwana da safe a hadu. Hajiya Saratu ita kadai Sukairaju ya kai gidansu Hauwa bayan ya zartar da umarin da aka yi masa.

masu karanta littafin nan ba ku biya ni hakkina ba ina binku bashi ba wai don baku dashi ba ne. Na kudi ne yi kokari ki sauke hakki domin abu kad'an da ake rainawa sai ya hana ki kwanciyar hankali. Allah Ya datar damu.

Dama Hajja ta sanar da Inna Uwani zuwan na su don haka da ta ga Hajiya saratu ita kadai ta shiga tambayarta mai gayya mai aikin ta ce mata tare suke Amma da safe zai shigo kamar yadda ya fad'a. Inna Uwani sosai ta marabceta ta yi wanka ta yi salloli ta ci abinci Hauwa tana kwance a cikin d'aki ba ta fito ba ta gaisheta ba kuma tana jin motsinta. Itama kuma inna Uwanin ba ta yi mata magana ba ai ko babu komai tunda ta ganta a gidan

tasan akwai dalilin zuwanta Kuma ko banza ta girmeta ta kuma girmi mijin nata yayarsa ce.
Hajiya Saratu abin ya yi mata ciwo sosai amma sai ta share tunda sulhu suka zo bai kamata ta yi wani abin da zai sake harzuka zuciyoyinsu ba.
Da yake d'akuna uku ne a d'akin d'aki daya inna Uwani ta gyara mata da katifa da mashinfidi ta shiga ta kwanta sai da asubahi tukkuna da suka gaisa suka fara tattauna maganar inna Uwani tana fad'in." To dukansu dai babu yaro idan sun yi hakuri sun rungumi auransu sai sun fi kowa mora kuma yaransu su tashi cikin annashuwa tare da tsalle da dara a gidansu domin duk inda uwa da uba suka rabu yara sukan kasance a lalace. Kuma ban ga dalilin da zai sanya Tajo ya dinga kwashe musu yara yana bawa wata ajiya ba, Saratu ki dubi lamarin nan fa da kyau ki ga ni akwai son zuciya, ba ni so na fiye magana a ga kamar ina goyon bayanta, tana da gaskiya a wannan ga'bar domin abu ne mai wahala uwa ta yarda a d'auki danta a bawa kishiyarta cikin gadara da iko, a kuma biyo ta da ba'kar magana da zagi."
Ta ce." Ni kaina ban goyi da bayan hakan ba Inna wannan dalilin ne ma ya sanya da Hajja ta ce masa ya zo nan din ya baki hakuri na ce ya bari mu zo tare domin bibbiyu tafi dad'i amma tsakani da Allah ita abinda ta yi ta kyauta Inna ki fadi gaskiya. Daga kowane bangare fa akwai lefi ko musulunci abinda ta aikata rashin imani ne da yin butulci ga Allah."
Inna Uwani ta ce." Umm! to ni dai gaki nan ga Hauwa Saratu idan tana ganin ta gaji da zama da Tajo bisimillah sai ta share d'aki ta zauna. Idan kuma za ta koma  auransa sai ki tambayeta ni dai babu wanda ya isa ya shiga tsakanina da 'yar uwarta a cikinsu."
Tana gama fad'in haka ta tashi tana fad'in. A dama miki kunu  ko kuma shayi za ki sha."
Ta ce." Kunun dai zai fi dama-dama Inna amma a turo mini Hauwan mu yi magana."
Ta juya ta fita tana fad'in." To bari na turo miki ita."
Ta shigo sanye da hijabi  babu yabo babu fallasa ta zaune gefan katifar da take zaune ba ta kalle ta ba ta ce." Ina kwana."
Hajiya Saratu ta'ki amsawa tana fad'in." Ba zan amsa ba Hauwa ai kin nuna mini matsayina kamar ni na zo gidanku domin ke amma har na kwana ban isa ki fito ki gaishe ni ba, ke ba za ki canza dabi'u ba ko."
Ta yi shiru ba ta ce mata  komai ba. Sai ta girgiza kanta tana fad'in." To magana ce akan abinda yake faruwa ta kawo ni nan, Hauwa duk wani abu da ki ke jin an yi miki ki yi hakuri ki koma dakinki domin shine farincikin iyayenmu, tare muke da Tajo nasan an jima kadan zai shigo, ya tabbatarwa da Hajja cewa ya mayar dake tun kafin ki haihu kin ga yanzu baki da wata hujja da zata hana ki komawa." Ta nisa kafin ta cigaba da cewa." Yanzu ke ba ki ji kunya ba a ce bare wad'anda aka auro a waje sun fi ki matsayi da shiga zuciyarsa. Ke ya kamata fa ace kin fifita a cikinsu amma kina wasa da damarki. Zan gaya miki gaskiya ba ki kyauta ba, abinda ki ka yi ba daidai ba ne, kuma kin ba mu mamaki, yanzu Hauwa ko da babu aure a tsakaninki da Tajo ba za ki iya kula masa da yara ba? Ko daga waje ya auro ki bai kamata ki yi abinda ki ka yi........... Ta katseta kafin ta kàrasa tana fad'in." Anti Saratu

ban ga lefinki ba don kin kare shi, ai nasan babu wanda zai ta'ba goyon bayana balle a nuna masa cewa bai yi mini adalci ba, ya kyare ni, ya tsangwame ni a gidansa, ya fitar da hannu ya dake ni, ya kira ni jahila mara tarbiya duk a gaban matayensa . Ya nuna musu kan dole yake zaune da ni, na haihu ya nuna mini iko akan abinda na haifa baiwa ce ni, ko kuma jaka ce, ai kudi na hauka ba ne, kuma itama Amina ai ubanta talaka ne  mai yasa ya fifita ta a kaina, mai yasa yake rangwanta mata.  Idan ya daukaki Maryam domin yana ganin tana da dukiya daidai take da shi, ai ta wani gefan  na fi Amina usuli tunda kaf dangin mahaifina fana uwata babban family ne, ya za a yi na yi rayuwar 'yanci da jin dadi a tsakanin kishiyoyin da aka nuna sune suke da mutunci a kaina."
Ta sassauta tana fad'in." Ita Aminar ce ta gaya miki cewa ta daban ce a wurinsa. Ko kuwa kina ganin ta wuce ya yi mata shegantaka idan har tsiyarsa ta motsa, to idan har ma kina tunanin haka ki bari domin kuwa babu wata mace da za ta gaya miki cewa mijinta na yi mata yadda take so ba tare da yana guma mata ba. Shiyasa ai nake fad'in na raina wayonki da gogewarki tunda har ki ka kasa karantar yanayin zamantakewa da wanda Allah Ya had'a ki zama da shi, ba wai ina fad'a miki haka ba ne saboda Ina kin'ki ko Kuma na nuna miki cewa d'an uwana nake goyawa baya. Shima mun nuna masa kuskuransa kuma ya d'auki niyyar gyara tunda har ya tako kafarsa garin nan to tabbas ya aminta da cigaba da zama dake. Hauwa ki yi karatun ta nutsu kowane aure akwai kalubale a cikinsa ki kara hakuri akan wanda ki ke yi, ke da dan uwanki kada ki bari abokanan zamanki suga wallenki har su yi miki dariya a fakaice. Har yanzu
Amina da Maryam sun fi ko way........" Kin ga anti Saratu don Allah ki kyale ni na ji da bakincin da yake damuna kada ki kara mini dama tuntuni ni duk abinda zai faru ba kya ba ni goyon baya kin sha nuna mini Amina ta fi ni mutunci  gaskiya ba zan iya komawa ba shiyasa ma na ajiye masa d'ansa ya nemi mai shayarwa."
Cike da tsananin bacin rai Hajiya saratu ta ce." To shikkenan Hauwa kada Allah Ya sa ki koma din, ki yi ta zama tunda haka kike ganin ya fi miki, yaro zai rayu ko dake ko babu ke, dana san abinda za ki yi mini kenan da ban shiga sabgarki ba, duk abinda zai sake biyo baya ba zan sake sanya bakina ba ki yi yadda kike ganin ya yi miki."
Ta mike tsaye tana fad'in. Gashi na yi hakan shine ya fi mini kwanciyar hankali da nutsuwa ba zan iya zama dashi ba idan yana tare da wannan tsohuwar mushirkar matarsa."
Ta ce." Ki je mana kada ki zage ni Hauwa  tunda kin yankewa kanki hukunci wanene ya isa, Allah Ya bada sa'a."
Ta kama hanyar fita bayan ta ja mata wani  tsaki mai tsayi wanda ya yi mata mutukar ciwo a zuciya. Hauwa ce yau tsare kerere a gabanta tana gaggaya mata magana har da tsaki abin ya tsaya mata ranta sosai har da 'yar kwallarta ta goge tare da d'aukar wayarta dake gefenta.
Tana kiransa ya daga Yana fad'in." Na shirya tsaf gani nan zuwa. " Cikin rawar murya ta ce." A a, ka zauna anan hotel din, ko da yake ba zan hana ka

zuwa ka gaishe da Inna ba, da sai na ce ka zauna an jima kadan zan yi wanka ka turo Sukairaju ya d'auke ni."
Jikin yadda muryarta take rawa ya sanya ya ce." Wani abin ne ya faru?"
Ta gyad'a kanta tare da sanya yatsu ta goge hawayen da ya zubo mata. Domin daga zarar ta tuna tsakin wulakacin da Hauwa ta yi mata sai ta ji wani tashin hankali tunda take ba a ta'ba yi mata wannan iskancin ba da 'ya'yanta magidanta da kuma shekarunta, lallai karfin zumunci ya shallake komai amma da ba don haka ba tabbas da Hauwa ta raina kanta a yau, shikkenan daga gyara kayanka, Hauwa bata da mutunci ko kad'an.
Ta ce."Bari kawai Tajo, Allah dai ya kyauta shine abinda zan ce."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Zan turo Sukairaju ya d'auke ki yanzu kawai mu wuce Allah shikkenan."
Ta amsa da "Amin." Kafin ta kashe wayar a sanyaye wanda Yayi daidai da shigowar inna Uwani da jug na kunu da kwanon silva sabo dal dashi da k'osai a ciki. Ta ajiye gabanta tana fad'in.'' Ga kunun Saratu k'osan ma da zafinsà na d'ora miki ruwan wanka yanzu nan.
A tak'aice ta ce." To na gode Inna Allah Ya saka da alheri.'' Har ta juya za ta fita sai kuma ta tsaya tana fad'in.'' Tajon zai shigo din ko domin yanzu nan Baffansu Tijjani wanda gidansa yake kallon namu ya shigo yana gaya mini zai fita aiki na ce ya d'an jira domin su samu damar tattaunawa akan abinda yake faruwa."
Ta ce." E, zai shigo din ya jira shi" Ta fad'i Hakan ne domin ba ta san me za ta ce mata ba.
Sai ta juya ta fita da sauri tana fad'in." Bari na gaya masa to."
*2K Complete a telegram. Normal What'sapp group kuma 1k via 0542382124...Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*GARKUWAR MATA ✍*
*BINTA UMAR ABBALE*
*TALLAH* https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma

Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*PAID BOOK 2K COMPLETE ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1K VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*

Kiranta kawai ya yi a waya ya gaya mata ga Sukairaju nan ya turo domin d'aukarta.

Sukairaju da ya zo ya shiga cikin gidan tunda akwai sabo dalili amintaccen yaronsa ne duk a cikin masu yi masa hidima. Suka gaisa da inna Uwani har tana yi masa tayin abun kari ya ce a koshe yake ya fita ya tsaya jikin mota yana jiran fitowar Hajiya Saratun.

Ta fito cikin shiri tunda dama ta yi wanka ta kintsa sama-sama ta iya yin karin kummalo dalilin takaicin rashin kunyar da Hauwa ta yi mata. Inna Uwani na zaune a tsakargida tana gyara kayan miya Hajiya Saratu ta fito tana fad'in." Inna tafiya zan yi."

Ta juya da sauri tana fad'in." Tafiya kamar Yaya Saratu ina Tajon yake ne shi ake jira domin Tijjani har ajiye aikinsa ya yi saboda ya gan shi su yi magana."

Ta ce." To ni kam ban san me zan ce miki ba Inna amma ina tsammanin Hauwa ba zata koma ba domin ta gaya mini d'azu da muka yi magana. Amma ki sake tuntubarta."

Inna Uwani ta saki baki tana kallonta a sanyaye ta furta." Haka tace miki ba zata koma ba Saratu?" Ta gyad'a kanta tana fad'in." Ai da hakan ta gaya mini da sauki Inna ba zai dame ni ba amma babu komai Allah Ya sa hakan shi ya fi alheri, Allah Ya raya yara."

Daga haka kawai sai ta kama hanyar fita. Inna Uwani ta bi bayanta tana fad'in." Ina Tajon yake ba zai shigo mu gaisa ba kenan?"
Hajiya Saratu ta yi shiru ba ta ce mata komai ba. Haka ta fice daga gidan inna Uwani na le'kenta Sukairaju ya bud'e mata mota ta shiga ya ja suka bar wurin. Jikinta sanyi kalau ta koma cikin gidan kamar mara lafiya.
Shi dariya ma abin ya bashi da Hajiya Saratu ta gaya masa abinda ya faru. Ya dinga gyad'a kansa yana jimanta fitsarar Hauwa ko shi ba ya iya tsalleke Umarninta kuma baya iya duban idonta ya yi jayayya da ita, sannan kuma yakan yi aiki da shawarwarinta amma yau an wayi gari Hauwa d'iyar cikinta ta ci mutuncinta saboda wani dalili. Abin ya ta'ba shi sosai mussaman yadda ya ga yanayin Yayar tasa ya yi tabbacin abin ya yi mata ciwo a rai. In banda umarni ne na iyaye bai ga dalilin da zai sanya shi zuwa bikon Hauwa ba balle rayuka su b'aci zahiri kuma ba a tara sani ga Allah da ya san abinda zai biyo baya kenan da bai aminta da auranta ba.
Tun mota suka yi magana da Hajja shi ya gaya mata cewa zai wuce Bunkure gidan Malam 'Daha malamin mahaifinsu  wato Alhaji Ibrahimu. Yana nan ya tsufa sosai amma da yake tsufan ya wanzu tafarkin addini da karatun al'kurani jin sa da ganinsa duka ba su raunana ba. Sai dai matsalar kafa da ya samu amma baya ga haka babu wani abu da ya samu tawaya a tare dashi sai tsufa wanda wajibi ne ga kowane musulumi. Tun yana saurayi rabonshi da ziyartar malamin yanzu kam ya zame masa dole domin yana buk'atar addu'a bayan wadda yake yi akan kansa.
Sukairaju na sauke Hajiya Saratu a gidanta suka d'auki hanyar kauyen bunkure kamar yadda ya niyyata. Da k'yar ya iya sheda gidan dalili yawanci gonakin da suke garin an sayar an yi gine-gine na zamani tunda yanzu an samu cigaba a ko'ina kusan rabin garin ma ya zamananta da dama wasu na sauya fasalin gidajensu zuwa na zamani.
A can daga gefe Sukairaju ya ajiye motar amma bai fito ba yana ciki a zaune dalilin ganin yadda jama'a suka fara taruwa masu wuce wa suna tsayawa. Ya ce da Sukairaju ya yi sallama a kofar gidan Malam din haka kuwa ya yi ya dinga kwad'a sallama wani magidanci ya fito cikin yar shara  da fatanya a kafadarsa. Suka yi musabaha kafin ya tambaye shi. Ya ba shi amsa da eh gidan Malam 'Daha ne. Sai ya nuna masa motar yana fad'in." A gaya masa ba'ko ya yi Alhaji Tajuden ne na Alhaji Ibrahimu dambatta wato abokinsa da ya rasu."
Mutumin ya washe bakinsa kafin ya nufi wurin motar da saurin gaske. Sukairaju ya bi shi cikin gaggawa ya yi saurin tare shi.
Duk abinda suke yi yana kallonsu sai ya sauke gilashin motar fuskarsa a sake ya furta." Sukairaju matsa masa hanya mana mutumina ne."
Da sauri Sukairaju ya bashi wuri shi kuma ya kàrasa bakin motar yana ta dariya  tare da mamakin ganinsa. Ya bude motar cikin sauri ya fito ya rike hannunsa yana fad'in." Malam Rabi'u."
Ya ce." Naam Alhajin Allah dama za mu sake ganawa."
Yana dariya ya ce." Allah ya nufa gashi na ziyarce ku, na zo wurin Malam ne."
Ya gyad'a kansa yana fad'in" Ya bayan rabuwa Alhaji ya harkoki da jama'a Ubangiji Allah Ya taimaka ya kara suttura."

Ya amsa da "Amin Malam Rabi'u ya iyali fatan kowa lafiya?" Ya ce." Alhamdulillahi mata na hud'u ina da yara ashirin da biyu."
Cike da mamaki ya ce." Mata hud'u yara ashirin da hud'u Rabi'u?"
Sai ya kyalkyale da dariya yana fad'in." Kwarai kuwa Alhaji yanzu haka akwai shida mata dana aurar da su, suna d'akin mazajensu cikin aminci."
Ya gyad'a kansa yana jimanta karfin hali irin na mutanan k'auye gashi dai bashi da wani karfi irin na su amma ya ajiye mata hud'u da tarin yara."
Ya ce." Ka burge ni da gaske Rabi'u kuma kai namiji ne, yanzu dai ka yi mini jagora wurin Malam na zo mu gaisa ne."
Ya ce." Ka kyauta sosai kuwa domin idan ban mata ba yanzu ka kai sama da shekara asirin rabonka da garin nan tun marigayi yana raye."
Ya furta." Tabbas hakane domin karshen zuwan da muke yi tare da shi ne, tun bayan rasuwarsa kuma Allah bai nufe ni da sake zuwa ba."
Suka nufi cikin gidan a tare suna magana cike da jin dad'in had'uwa. Babu girman kai ko kuma nuna ni isheshshene yanayin yadda ya gaisawa da jama'ar da suka tsaitsaya yana ta d'aga musu hannu haka suka shiga gidan da aka narka 'kasa irin ta da mai d'anko wurin gida shi. Gidan mai yalwa ne sosai irin dai ire iren gidajen Malaman addini mussaman na karkara
har yanzu yana nan inda yake sai dai kwaskwarima da aka yi wa wasu guraran dalilin wasu daga cikin yaransa a ciki suke zaune da iyalinsu. Amma kuma sun gyarawa mahaifinnasu bangaran nasa tunda da alama yana yin manyan ba'ki mussaman abokai ko 'ya'yansu tunda fitacce malamin addinin musulunci ne da har yanzu tafsiri da karatun al'kurninsa ke yawo a wasu gidajen redion.
Koda suka shiga wurin nasa yana zaune kafarsa ta k'wanshe da al'kur'ani kirar warshu a hannunsa yana karatu babu wata gigita ta tsufa ya gane wanene a gabansa.
Rabi'u yana fad'in." Malam ga Tajuden na Alhaji Ibrahimu na kawo maka."
Ya yi dariya irin ta manya kafin ya ce." kuna shigowa na gane shi ai ko baTajudden na Alhaji Ibrahimu ba."
Ya ce." Ni ne Malam ina fatan na same ku lafiya ya bayan rabuwa kuma?" Ya amsa da "Alhamdulillahi ya iyali ya jama'a ya harkokin ina Hajiya Halimatu?" Yana nufin Hajja kenan.
Ya ce." Tana nan lafiya lau ta ce a gaishe ka da kyau Malam."
Ya gyad'a kansa tare da fad'in." Ina amsawa na kuma ji dadin ganinka Tajuden za mu sake saduwa kafin Allah Ya yi ikonsa."
Ya furta." In sha Allahu rabbi zan dinga ko'karin ganin na kawo ziyara Malam abubuwa sai a hankali."
Ya gyad'a kansa yana murmushi kafin ya ce."Allah Ya taimaka ya bada sa'a, na gode sosai Allah Ya yi albarka."
Ya amsa da Amin suma Amin kafin wajan ya d'auki shiru Malam Rabi'u tuntuni ya fita. Malam din ya ce." Akwai abinda yake tafe da kai ne?"
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Kwarai kuwa Malam muna buk'atar addu'a akan komai duk da muna yi akan kanmu, amma a kwanakin nan abubuwa sun yi yawa mussaman 'bangaran iyalina a taimaka mana da addu'a Allah Ya warware mana."

A nutse ya ce." Za a yi in sha Allahu akwai buk'atar ka tsananta addu'a akan kanka, daga nan zan sanya al'majirai yin saukar al'kur'ani tsayin kwanaki bakwai sai ka yi sadaka, Allah Ya warware."
Ya amsa da "Amin Ya Malam na gode sosai Allah Ya kara girma."
Ya furta." Za ka shiga ka gaisa da mutanan gidan ko?"

idan kin san kina karanta book din nan ba ki biya ni hakkina ba to Ina binki bashi.

Ya yun'kura domin tashi Yana fad'in." E, zan shiga Malam zan yi magana da Rabi'u akan abin sadaka sai mu ga yadda za a yi."
Har ya juya zai fita ya dakatar da shi ya tsaya sai ya ce." Ya iyalin Tajuden su nawa ne yanzu yaranka kuma nawa?"
Ya ce." Allah shi gafarta Malam su uku ne yara kuma ina da biyar rayayyu d'aya ta rasu."
Ya ce." Alhamdulillahi Alhamdulillahi Ubangiji Allah Ya yi musu albarka, Allah Ya raya mana su bisa tafarkin addinin islama. Idan har kana da buk'atar cika sunnar Annabi tunda su uku ne ka zo nan na zaba maka daya daga cikin yarana biyu da suka rage mini. Hakika ina sha'awar tabbatuwar zumuncina da Alhaji Ibrahimu. Duk da fad'in Allah ne kuma sunna ce mai kyau amma ba wajibi ba ne, abinda magabatanmu suka d'ora mu akai kenan lallai k'arshen duniya mata za su yawaita yayin da mazan auran za su yi 'karanci ko rashin ikon ga masu niyya. masu iko idan kuna da d'aya ku kara da ta biyu, masu biyu ku 'kara da ta uku, masu uku ku k'ara ku yi hud'u domin dakile mas'aloli masu yawa. Idan har ka niyyata tunda kana da iko kada ka manta ka zo nan zan had'a ka aure da nutsatstsiyar yarinya ko ba daga cikin yarana ba."
Cikin wani yanayin ya furta." To shikkenan Ya Malam idan da yiwuwar hakan in sha Allahu zan zo sai a san yadda za a yi na gode sosai, Allah Ya saka da alheri"
Ya amsa da "Amin cikin nutsuwa yana yi masa fatan alheri da sauka lafiya.
Yana fita ya ciko karo da Rabi'u a tsaye ya ce ya yi masa jagora cikin gidan domin su gaisa. Ya dinga mamakin yadda gidan Malam 'Daha
ya cika da tawagar yara 'yan mata da masu tasowa maza da mata sai iyayen tukuwane kangama-kangama dama can sanin da ya yi masa mutum ne mai arzikin gona ki a k'auyen don haka matsala ta abinci ba zata ta zama barazana a gare su. Malamin mahaifinsa ne kuma akwai abota sosai sai dai kowa tsarinsa daban. Mahaifinsa ko a can baya yana da wayewa sosai ta fannin boko da kuma addinin daidai gwargwado Hajja ita kad'an ta rayu bai ma ta'ba yun'kurin karin aure ba har ya rasu su biyu ya haifa. Shi kansa bai taba tunanin zai iya ajiye mata uku ba domin yadda ya tsara rayuwarsa tun daga kuruciya Samira kadai ta ishe shi, sai gashi Allah Ya na ta juya lamarinsa.
Har gajiya ya yi da amsa gaisuwa domin dai daga sashe sashe ake zuwa gaishe shi. Rabi'u ya riko hannunsa suka fita duk da haka wasu daga cikin yaran sai da suka biyo bayansu.

Bakin motarsa kuwa jama'a ne a tsaye Sukairaju yana ta fama da su. Daga bakin kofar  gidan Malam din suka tsaya a  dan gajiye yake  fad'in." Rabi'u kana da asusun ajiyar kudi ko?"
Ya ce." E, da akwai sai ya fito da wayarsa ya mika masa yana fad'in." Bismillah yi sauri sanya mini lambar a nan zan tura abin sadaka a bawa Malam sannan abinda ya yi saura ka yi amfani dashi a kuma sallami iyayenmu da k'annanmu da suke cikin gidan a ba su su sha ruwa."
Ya kar'bi wayar da sauri yana fad'in." To Allah Ya saka da alheri mun gode Allah Ya kara arziki Alhaji."
Bai ce komai ba har gama ya mika masa waya ya kar'ba a tsaye a wurin ya tura dubu dari biyar sannan ya bashi wayar a gain ya ce ya sanya masa lambar wayarsa domin su dinga gaisawa."
Ya kar'ba a karo na biyu ya sanya masa lambar shi kuma ya yi serving da Malam Rabi'u Bunkure.
Da haka suka yi  sallama cike da girmama juna. Sai da suka fita daga karkarar tukkuna Sukairaju yake tambayarsa ina suka nufa domin shi duk a tunani shi zai sake kwana a kono din ganin bai fiye son tafiyar mota ba. Ya ce." Mu d'auki hanyar gida kawai yau komai dare a gidana zan kwana Sukairaju na huce gajiyar gabad'aya."
Aikuwa da azama ya d'auki hanyar garin abuja kamar yadda aka bashi umarni.
Ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya d'an gyara zaman shi a mota yana nazarin maganar Malam 'Daha wai ya zo cikin karkara ya nemi aure domin cika ta hud'u. Gabad'aya ma shi yanzu babu wannan lissafin a tare da shi bai sani ba ko nan gaba. Gabansa ya fadi lokacin da ya tuna iya rigimarsa Amina tunda suka yi sallama jiya sau daya suka yi waya da daddare kafin ya kwanta ya kira ta domin gaya mata ba zai dawo ba sai gobe. Yana duba wayar ya ga kiranta ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya sanya wayar a kunnansa Amina ta tsaya masa ransa sosai shi kansa ya tabbatar da haka...✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
*TALLAH!* https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su

dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Paid book ne 2k complete a telegram Whasap guruf 1k via 0542382124....Binta Umar gtbank*
*07084653262*
Muna tare da yara falo wai sun zo ganin 'kaninsu domin babansu ya gaya musu sunansa Sultan falon ya kacame  Husaina da Minal har da kokawa ban ankara ba sai kukan Minal na ji da k'arfi lokacin ya yi daidai da fitowar Baba Tabawa daga d'akinta. Kukan Minal din ya zaburar da yaron shi ma ya tsanyare da kuka Baba Tabawa fadi take "A kul cizo ko Usai ba ki san 'kanwarki ba ce, ka da na sake gani kin yi cizo."
Na juya da mamaki ina kallonta yayin da nake jijjiga yaron na ce." cizonta ta yi?"
Hassana dake tsaye a gefe ta ce." E, ni ma tana cizo na ko Yaya?" Ta fad'a tana kallon Khalil da yake zaune  hankalinsa kan tibi domin shi duk rigimar d'aukar yaron da suke yi ban dashi da suka shigo dai ya zo ya tsaya kusa da ni bayan mun gaisa har yana tambayata sunansa Sultan ko na ce masa eh daga haka sai ya je ya zauna. Yana da nutsuwa sosai kuma bashi da hayaniya irin ta 'kuruciya.
Ya yi shiru bai ce komai ba wata'kila bai ga lokacin da ta yi cizon ba shiyasa bai yi magana ba.
Na ce." Kai cizo take yi dama?"

A hankali ya ce." Idan suna fad'a ba, itama Hassana ai mazilinciya ce ita ta koya mata cizon don ta fi k'arfinta"
Na dube ta ta yi tsuru-tsuru! domin da alama ba a saba yi mata fad'a ba ko nuna mata abinda take yi kuskurene. Fad'an da Baba Tabawa ta yi mata ya sanya ta kyakykya'be fuska za ta yi kuka.
Cikin tsawa na ce." Zo nan!" Ta'ki zuwa hawaye tuni sun 'kwace mata. Na ce." Ba za ki zo ba?" Ta ma'kale kafada tana kuka."
Na mi'kawa Baba Tabawa yaron ina fad'in." Ki mayar da shi baya wata'kila ya koma baccin." Hassana ta je da sauri tana fad'in." Baba ba ni shi na d'auke shi."
Cikin zare ido na ce." Matsa ki ba ni wuri babu wanda zai d'auke shi ai tunda ba za a ce ku bari ba."
Ta koma ta zauna jikinta a sanyaye. Na janyo Minal da take shashshekar kuka na d'orata saman cinyata Ina rarrashinta har ta yi shiru na bud'e mata game a wayata tana wasa.
Yadda suka takure a wuri d'aya hakan bai sanya ni na ji tausayinsu ba abinda ya dame ni shine rashin jin magana d'aya domin tun kafin a kai ga cizon nake ce musu su nustu zan bawa kowa yaron ya d'auke shi ban ankara ba har an kai ga cizo.
Na mik'a hannuna da sauri na janyota gabad'aya ba su ankara ba sai suka fasa ihu a tare domin yadda na janyo Usai din shi ya zaburar da 'yar uwata Abinda ba su saba dashi ba kenan
Khalil ya zubo mini ido da yanayi na damuwa kamar ya hana ni. Na kama kunnanta na mur'de shi da k'arfi. Ta tsala ihu! sai hawaye shar-shar! Baba ta fara ko'karin kwaceta. Na kai mata rank'washi da d'aya hannuna ina sake murde fatar kunnan na ce." Wallahi duk ranar da na sake ji an ce Usaina ta yi cizo zan sanya reza na yanke harshenta Khalil ka zama sheda idan ta yi ko a gidan Momin ne ka zo ka gaya mini." Da sauri ya ce. "Ba za ta sake ba Mama ki yi hakuri kin ji."
Na cika mata kunnan ta matsa gefe kusa da 'yar uwar da take tayata kukan suka jeru suna yi cikin jan hanci da sauke ajiyar zuciya."
Kiran da ya shigo wayata ya katse maganar da muke yi da Baba Tabawa akan abin duk yaro mai cizo ai babu yadda za a yi yayi farinjini ko yanzu hannun Minal ya yi shedar ha'kora ina dalili.
Koda na duba maigidan ne. Na daga lokacin kukan yaran ya hana ni jin abinda yake fad'i mi'kewa na yi na nufi d'aki ina fad'in." Ina jinka ina yini?"
Ya amsa a tak'aice kafin ya ce." Wacece take kuka Hassana ko Usaina?" Kai tsaye na ce." Dukansu ne?" Ya yi Jim kafin ya furta." Akan wane dalili Amina?"
Na ce." Fada suka yi har da cizo shine don an yi musu fad'a suka had'a kai suna kuka?"
"Idan wannan fad'an ne a junansu sun saba yi ai."
Ya fad'a da yanayi na b'acin rai a maganarsa.
Na ce." Da sau'ki idan a junansu suka yi tunda tare suka rayu ko a ciki daya. Usai ce ta ciji Minal a hannu?"

Ya yi shiru bai ce komai ba haushi ya ji da alama sai abin ya ba ni mamaki da dariya. A gajarce na ce." Ka taho ne?"
"E, kin ga Amina kada ki sake dukan yaran nan ba na so na gaya miki?"
Na ce." Haka na ce maka na dake su? fad'a fa kawai na yi mata ita mai cizon shine ita abokiyar tagwaitakartata take tayata kuka bayan Kuma ita din ta tabbatar mini da cewa dabi'ar yar'uwartata kenan cizo a ganinka d'abia ce mai kyau?"
"Na ce dai kada ki sake dukansu ban ce dabi'a ce mai kyau ba fad'a ya isa ban da duka."
Na ce." To." kawai na yi shiru ina mamaki.
"Gani nan kan hanya in sha Allahu ki yi mana addu'ar sauka lafiya."
Na ce." Allah Ya kawo ka gida lafiya."
Ya amsa da "Amin. " Kafin ya kashe wayar na fita falon ina mamaki ashe zai sake ru'banya domin babu kowa a falon har Khalil din. Na bi Baba Tabawa kicin ina fad'in.'' Ina yaran suke?"
Ya juyo tana kallona kafin ta ce." Au ko sun tafi babu sallama."
Na ce." Da alama gashi na fito babu su a falon.
Sai ta sanya dariya tana fad'in." Kai jama'a yaran yanzu ba sa son fad'a, wato fushi suka yi."
Na gyada kaina ina fad'in." Kada Allah Ya sa su 'kara shigowa gidan." Na fita daga kicin din raina a b'ace ni ba za a yi wannan sakarcin da ni ba. Daga jin kukan yara ya yi wani kicin-kicin yana fad'in magana a kumbure kada a dake su, aikam sai dai ba su yi abin dukan ba.

Shigar k'ananun kaya na yi domin tar'barsa ina da ragowar kwana daya tunda shekaran jiya kawai muka kwana dole anan wurina zai kwana. Na tsaya gaban madubi ina duba kaina na juya nan na juya nan har abin ya so ya ba ni dariya ni kaina ba kasafai nake son sanya rriga da wando matsatstsu ba don sai na dinga ganina kamar wata inyamura yanzu na dinga kallon kaina a madubi ina tuna wata jarumar finafinan kudu na manta sunanta amma tana da wani irin hips mai tudu da mutukar daukar hankali. sam bata da kyawu a fuska amma tana da dirin jiki mai kyau. Kai na ji dadin maganin tumbin nan da nayi amfani da shi domin yanzu ina yin gayu sosai na matse ko'ina na jikina ya fita yadda ake so maganin ya daidaita mini yanayin jikina kwarai......08089965176 ga masu buk'atar su tuntubi wannan lambar.

Misalin tara da arba'in na dare ya kira ni yana gaya mini ya d'an jima kad'an da dawowa yana gidan Momi zai shigo zuwa an jima na ce to shikkenan.
Na bud'e wayata sakkonin Sahura suka shigo rututu na shiga ina dubawa ina kuma saurararan voice note din da ta turo mini yanzu haka tana gidansu. kuma ta sanyawa gidan sabon kwado Idiris sai dai ya nemi makwanci."
Cike da mamaki na kira wayarta.
Tana d'agawa na ce." Sahura me ya yi zafi haka? yanzu har sai sai ta kai ki ga tafiya gida ba za ki yi hakuri ba."
Ta furta." Amina wallahi na rantse sai dai ya zab'a ni ko matar da zai auro da gaske fa aure zai yi wallahi da idona na ga yana had'a lefe."

Na ce." To shine me wai? ke ba za ki iya ha'kuri na d'an wani lokaci ba Hajiya don Allah kada ki ba ni kunya mana."
Cike da damuwa ta ce." Ke ma kin san babu adalci dangane da abinda Idiris yake ko'karin yi mini ko Amina."
Na danne dariyar da take so ta kwace mini na ce." Na sani to amma ba mu da yadda za mu yi, ba za mu hana shi ba amma ai bari ba shegiya ba ce idan ta shigo kudin suka kare sai ta ga kwakwar da ake ciki a gidan. Ki yi hakuri don Allah ki koma. Yanzu ina yaran suke?"
Ta ce." Suna can gidan Babarsa." Na ce amma abu bai yi dad'i ba wallahi, ki bari da safe za mu yi magana in sha Allahu gabad'aya kin tayar mini da hankali wallahi."
Ta yi 'kwafa ba ta ce komai ba.
Na ce." Da safe zan kira ki in sha Allahu rabbi." Ta ce." To shikkenan."
Na kashe wayar na ajiye Ina mamakin yadda ta tayar da hankalinta wato idan ka ga mutum bai yi abu ba to bai zo kansa ba sai na tuna lukuta da dama da abubuwan da suka shude kai kishiya abar gudu ce, su kuma mazan suna fad'in abokiyar zama ce.

To cikin shan k'amshi ya shigo mini  ganin haka ya sanya ni ma na kama kaina. Na yi masa sannu da zuwa a takaice bai zauna ba ni ma ban yi masa tayin zaman ba tunda dama sai ya so yake zama har ma ya kwana d'akin nawa. Na dube shi yana ta jin haushi na yi tsai ina nazarin abinda ya sanya shi shigo mini haka idan don na yi wa yara fad'a yake jin haushi to yanzu kuwa na fara wallahi.
Ya juya zai fita yana fad'in." Ina sama ki zo?"
Ban amsa ba har ya fita. Na ja tsaki ina fad'in." Aikin banza harara a duhu. Sai dai ya yi kusan minti ashirin da fita na bi bayansa. Yana  can kan kujera daga gefe yana duba Loptop dinshi na shiga.  Ya amsa sallamata yana kallona har na je na zauna kujerar dake kallonsa bai d'auke idonsa ba. Ni ma kallonsa din nake yi cikin yatsine fuska. Ya sassauta yana d'an murmushi ya ce." Yau kuma baturiya ki ka koma Amina?"
Na yatsuna fuska ban ce komai ba.
Ya ce." 'Dan taso ki zo nan."
Juyar da fuskata na yi ban ce komai ba kuma ban tashin naje din ba. Dole shi ya kashe Loptop din ya zo inda nake yana fad'in." Irin wannan gayun Amina ai ba zan iya komai ba."
Na ta'be baki uffan ban ce ba. Ashe karyar cin magani yake yi. Ya rike hannuna tare da ko'karin d'aga ni wai sai na tashi tsaye."
Na cire hannuna ina fad'in."Menene haka?" Ya lumshe ido kafin ya ce." To nuna mini kwalliyar na gani, na bawa idona hakkinsa."
Na dauke kaina domin ganin ya fara gigicewa. Ya d'ora hannunsa saman kirjina da suka dan taso ana ganin tsagarsu.
Na cire hannun da sauri ya sake jana da k'arfi har sai da na zamo daga saman kujerar na zauna kasan kafet tare da tankwashe k'afata. Saman kujera ya zauna ya sanya ni tsakiyar k'afafunsa ya rankwafo kaina tare da zuba gabad'aya hannayensa saman kirjina ya ri'ke da kyau. Dole babu shiri

na tashi tsaye abinda yake so kenan ya mike shima ya rike hannuwana da kyau yana kallona. Duk sai na tsargu na dinga kame-kame daga nayi yun'kurin zama zai tsayar dani.   Cikin iyashege ya fara dukan mazaunaina yana fad'in." Babar mota babbar giwa ba dai yaro. Hajiya da kanta wannan samun irinta sai an had'a da sallar dare."
Duk yadda na kai ga cin magani sai da ya sanya ni dariya na shiga bige hannunsa ina fad'in." Don Allah ka bari dukana fa kake yi a fakaice gaskiya zan rama wallahi."
Ya ci gaba da d'aka mini duka a mazaunai bai bari ba duk da buge hannunsa da na yi yana fad'in.'' Gaskiya na iya kiwo wallahi, wai tur'kashi Allah Ya ba ni wuyan d'auka."
Dariya na dinga k'yalkyalawa shima ya sa dariyar yana fad'in." Haba Hajiya ko ke fa, kin yi lefi kina ci mini kunu haka ake yi."
Ya rike hannuna muka zauna saman kujera yana yi mini wani irin kallo da na kasa tantance ko na menene a hankali ya ce." Kin yi mini kyau yau fiye da koyaushe na yaba sosai kuma zan bada tukwici. Na zuba masa ido ina kallonsa ya ciro wani zuben azurfa da yake yatsanshi na tsakiya zoben tunda na san shi dashi a hannunsa kusan koyaushe kamar k'ara masa kyau da sabunta ake yi azurface gangariya daga tsakiya an yi mata ado  cikin wani salo. Da yake siraran yatsu ne dashi ya sanya yana sa mini ya kama ya tsayana wanda ya zauna ya yi cif cif ya yi kyau sosai. Ya sumbaci hannun yana fad'in." Ga tukuici idan bai isa ba sai na sake bada wani abin."
Na dubi yatsana ina dan murmushi na furta." Aikuwa na gode sosai da wannan tukwici ya yi mini ba sai an bada wani ba."
Sai ya hade hannunmu wuri d'aya yana fad'in." Kin san wani abu?"
Na girgiza kai ina kallonsa ya ce." Kada ki sake dukan yaran nan ba ni so, a duk lokacin da wani abu ya shiga tsakaninsu ko suka yi abu na rashin kyautawa a zare musu Ido, a yi musu fad'a amma ban da duka ba na so, domin hakan ba tarbiya ce ba don wasu lukutan dukan yakan kangarar da yaro.
Na daidaita yanayina tare da fad'in. " Wai wanene ya gaya maka dukanta na yi? fad'a fa na yi mata na dan murde mata kunne shikkenan duka."
Ya ce." Ta gaya mini kin dake ta a kanta shin kin san illar duka aka kuwa?"
Raina ya b'aci amma na  danne na ce." Sai na dake a kanta domin na illatata ko?"
Ya yi shiru yana kallona. Na ce." Ni ban yi mata dukan da zai firgitata ba a gaban Baba Tabawa komai ya faru. Ba ni son cizo domin yana da illa sosai dole a ja mata kunne."
Ya ce." Ni ma ban hana ba, dukan ne kawai na ce ba na so kada a sake?"
A tak'aice na ce." To shikkenan." Domin maganar ta mutu kawai amma ba yadda za a yi Ina raye kuma ina gani su yi abinda ba shikkenan ba na zauna ina yi musu lako-lako ni kaina ba a yi mini irin wannan tarbiyar ba, ba kuma zan yi wa yarana ita ba.
Na ce." Ina Hauwa na d'auka tare za ku taho?''
Ya ce." Tana can gidansu wai ba zata dawo ba"
Da mamaki na ce." Ba zata dawo ba?"

Ya ce." Kwarai kuwa haka ta fad'a, na ce to shikkenan Allah Ya hada kowa da rabonsa."
Kawai sai na zuba masa ido da mamakin maganarsa wai Allah Ya hada kowa da rabonsa ya fadi hakan cikin kwanciyar hankali tabbacin abin bai dame shi ba. Ni Kam sam lamarin bai yi mini sugar ba. Na ce." Don girman Allah ka yi hakuri."
Ya dube ni da mamaki kafin ya ce." Ha'kuri ai na yi tunda har na mayar da ita amma ta ce a a, kuma ta yi mana shegantaka sai ta sha zamanta abinda ga matan nan da yawa me zai dame ni Amina."
Na ce." Amma dai ba kamar ita ba."
Ya ce." To yanzu ya za ayi?"
Kai tsaye na ce." Ta dawo dakinta don Allah."
Sai ya yi murmushi a hankali ya ce." To ki kira wayarta sai ki roke ta Ina ga haka zai fi."
Daga haka sai ya tashi ya nufi gado yana fad'in." Zo mu yi wata magana."
Na yi jim kafin na tashi na bi shi gadon ya janyo ni na kwanta a gefensa sai ya sanya hannu ya rungume ni sosai a jikinsa yana fad'in."Alhamdulillahi. Sai na rasa godiyar Allahn ta mecece haka dai muka raya daran cikin shau'ki da sakwarkwcewa. Da asuba yana fita salla ni ma sauka k'asa cikin gajiya da bacci a idona.
Sai da na yi wanka tukkuna na yi sallah na nemi gado na kwanta domin mugun bacci ne a idona wanda zai iya zame mini ciwo muddin ban yi shi ba.....✍

*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*

https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic

ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa

*PAID BOOK 2K COMPLETE ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1K VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*

Kirana da aka yi a waya shi ya tashe ni wajejan goma da ashirin da biyar na safe. Koda na duba lambace babu suna na daga tare da sallama sai na ji muryar Idiris mijin Sahura nan da nan na daidaita yanayina. Domin zahirin gaskiya ni ma haushinsa nake ji dangane da abinda yake ahirin aikatawa. Tabbas nasan kiran nasa baya rasa nasaba da matsalarsu. Muka gaisa jikinsa a sanyaye ya fara yi mini bayanin halin da ake ciki Sahura ta rufe gida sannan ta tattara yara da kayansu ta kaiwa mahaifiyarsa bayan tasan bata da k'oshin lafiya. Yanzu haka sai a shagon dake jikin gidan ya kwanta shagon da yarana suke d'inki kenan yana jadadda mini a cikinsu ya kwanta cike da alhini da damuwa. Ban katse shi ba har sai da ya kammala tukkuna na ce."
To wallahi ni dai Idiris ba ni da tacewa akan wannan lamari. Ina ganin ka kyaleta kawai tunda tafi buk'atar rabuwar sai ka je ka yi rayuwarka da sabuwar amaryarka yara kuma ai duk sun girma babu wanda za a yi wa wahala a cikinsu."
Da damuwa ya ce." Saboda fa kusancin da yake tsakaninku ya sanya na kira ki Amina, me yasa za ki gaya mini haka ke don Allah idan na ce zan rabu da Sahura ba za ki yi mamaki ba?"
Na d'an yi murmushi babu nisha'di na ce." Babu mamakin da zan yi Idiris abinda aure na mutum biyu ne idan ka gaji da ita zaka sawwa'ke mata mana ko kuma ka nemi hanyar da za ka k'untata mata."
Ya ce." Yanzu dai don Allah ki rarrasheta wallahi ba wai don na wulakantata zan yi auran nan ba. Ina son Sahura ina kuma buk'atar cigaba da zama da ita ki rarrasheta ki bata ha'kuri ta dawo mu cigaba da zama in sha Allahu babu abinda zai faru domin itama yarinyar da zan aura bata da matsala 'yar gidan tarbiya ce wallahi bata da fitina."
Na yi dariya ina mamakin maganarsa tun bai zauna da yarinyar ba yana shedar halayenta tabbaci kenan ba zai janye ba. Na ce." To shikkenan zan yi magana da ita zuwa an jima in sha Allahu."
Da sauri ya furta." Zan kira ki domin na ji abinda ku ka yanke amma don girman ki tausheta ta dawo na ware mata turmi biyu daga cikin lefen da nake had'awa sannan zan bata dubu hamsin sai ta sayi kayan kwalliya."
Na ce." To shikkenan. Da takaici na katse wayar ban tsaya na kàrasa sauraran karshen maganarsa ba. A tunana ai Sahura tafi karfin turmin

atamfa biyu da dubu hamsin, ita wahalar nawa ta yi masa tunda suka yi aure har yanzu ma cikin yi masa hidima take.

Da yammacin ranar muka yi waya da ita na gaya mata Idiris ya kira ni a waya akan abinda yake faruwa. Kamar yadda ya buk'ata din na fara rarrashinta da kawo mata misalai  ta yi shiru tana saurarena don har ina murna ina cewa ta sauko a zuciyata sai da na gama maganata tukkuna ta ce ." Ba ni buk'atar atamfofinsa ya ri'ke har da k'udin ya k'arawa amarya Amina, takarda zai aiko mini da ita yanzu zaman da nake yi kenan."
Na ce" Sahura akan kishiya dai idan ki ka kashe auranki na kusan shekara ashirin  da wani abu wallahi kin ba ni kunya kuma na raina wayonki, ki bari ta shigo mana ki ga kamun ludayin zaman. Haba don Allah ki jure mana."
Kashe mini wayata ta yi ta barni ri'ke da tawa a kunne da mamaki.

Bayan magriba Idiris din ya dinga kira wayata ina kan daddauma ina jan carki kamar yadda na saba. Koda na duba na ga shine na ajiye wayar kawai na cigaba da abinda nake yi shi kuma bai fasa kira ba. Hakan ya yi daidai da shigowar maigidan wanda shi ma tunda ya fita da asubahi bai sake shigowa ba.
Ya d'auki wayar yana dubawa sai ya kalle ni kaina a sunkuye kawai sai ya daga tare da sanyata a kunnansa jin muryar namiji na ji yana fad'in." Wanene?" ban ji abinda Idiris din ya ce masa. Na ji yana fad'in." Mijin Sahura ne to bari ta kammala tana azkar ne zuwa an jima sai ka kira."
Ya yi shiru na d'an wani lokacin kafin na ji yana fad'in." Amin Ya Allah, ma sha Allah, ka kira zuwa an jima kadan." Daga haka sai ya kashe wayar ya ajiye har na kammala na juyo ina dubansa ya ce." Mijin Sahura ne ya kira ki a waya ina fatan lafiya?"
A tak'aice na ce." Lafiya ba lafiya."
Ya dube ni sosai yana fad'in." Suna da matsala ne?"
Ina ko'karin cire hijabin jikina na furta." Aure zai ka'ra shine take bore har ta tafi gida."
Ya yi d'an jim kafin ya furta." Na kan rasa inda tunaninku yake tafiya wataran Amina, daga zai kara aure domin raya sunna sai ta ta tafi ta bar dakinta menene amfanin hakan."
Cike da takaici na ce." Ai ba a ce kada ya kara ba, ya bari ya tsaya da k'afafunsa tukkuna bashi fa da cikakkiyar
sana'a, wallahi Sahura wahala take sha a hannunsa kuma ta yi masa hallaci tunda suka faru a gidan haya suke shekara kusan ashirin da uku da auransu buge-buge yake yi itace karfin kula da gidan tun kafin ma ta samu aiki a kamfaninka haka take gwagwarmaya. Amma shine daka kawai an yi musu rabon gado ya samu miliyan takwas ko wata biyu fa ba a yi da raba musu kudin ba ya fara yun'kurin karin aure har yana tara lefe a dakinta. Ita kuwa ta kulle gidan ta gudu ta kai masa yaransa wurin Babarsa."
Dariya ce ta sub'ce masa ya dinga yi har ina mamakinsa na d'auka ai zai cigaba da goya masa baya. Ya ce." A lallai bai kyauta ba kuma da gaske bai yi adalci ba. Yadda ki ka gaya mini yanzu ai ita ta yi masa hidimar da ta zarce

ta miliyan takwas to me yasa tunaninsa bai kai ya saka mata da alheri ba sai da kishiya. Bai kyauta bai kuma yi daidai ba, in banda rashin tsinkaye ai ba aure ya kamata ya yi ba a yanzu ko?"
Da sauri na ce." Kwarai kuwa abinda itama take ji wa haushi kenan zai bata turmin atamfa biyu da dubu hamsin abinda ya kara ba ni haushi dashi kenan."
Ya ce." Kin ga kira mini Sahurar yanzu na yi magana da ita."
Na zauna gefansa ya miko wayata na lalubi lambata bugun farko ta daga cikin bala'i ta fara fad'in." Amina ki kyale ni don Allah idan har kin san ba maganar arziki za ki gaya mini ba, na gaya miki na gama yanke hukunci, idan kema za ki goyu da bayan Idiris din sai nasan a wani aji zan ajiye ki."

Ina binki bashi idan kin karanta ba ki biya ni hakkina ba

Na ce." Yi ha'kuri mai da wukar sis, Yallabai ne zai yi magana dake." Ta yi shiru ba ta ce komai ba sai na mik'a masa wayar da sauri ya kar'ba a nutse ya kira sunanta  "Sahura."
Ina ji ta amsa cikin ladabi." Na'am ranka ya dad'e ina yini?"
Ya ce." Lafiya lau ya kuke ina yara?"
Ta ce." Kowa lafiya lau Sir."
Shiru ya d'an biyo baya kafin ya yi gyaran murya ya ce." Kin san abinda nake so dake?" Ta ce." A'a. "
Ya ce." Amina ta yi mini bayanin duk abinda yake faruwa, ki yi hakuri ki koma dakin mijinki ki cigaba da kula da yaranki, shi kuma ki kyale shi idan har kina da hakki sannu a hankali Allah zai saka miki. Ni kuma zan yi miki alheri domin ki zauna a wadace cikin walwala  zan canza miki gida mai kyau sannan zan baki kudi ki dinga wata sana'ar a gefe sannan ki cigaba da zuwa aikinki kina taimakon yaranki da 'yan uwa, kada don mijinki zai kara aure ki yi fushi ki dasawa kan ki k'unci yaranki su shiga damuwa ki daure na wani lokaci komai zai wuce ."
A sanyaye ta ce." Na gode ranka ya dad'e, Allah Ya saka da alheri, shikkenan in sha Allahu zan koma kamar yadda ka buk'ata."
Cike da jin dadi kuwa ya furta." Ni ma na gode sosai Sahura, zan yi magana da Jamilu sakatare na nan kamfanin naku duk abinda yake da akwai zai yi miki bayani in sha Allahu maganar abinda na ce zan baki kuma za ki gani a daran nan."
Ta dinga godiya har muryarta tana rawa. Ya mik'o mini wayar na kar'ba a d'an sanyaye na ji dad'i sosai da ya shiga lamarin gashi har da alherinsa ko babu komai yana da lada a wurin Ubangiji.
Muka yi sallama da ita tana fad'in." Na kara yi masa godiya. Na dube shi a hankali na ce." Mun gode sosai Ubangiji Allah Ya saka da alheri."
Bai kalle ni ba ya ce." Ba ni details dinta yanzu ."
Ya miko mini wayarsa na kar'ba na sanya masa kamar yadda ya ce.
Ya ce." Ke nawa ki ka bata gudummuwa?"
Na ce." Gudumawa kuma?"
." Dannar kirji kuke cewa ko?"

Dariya na yi na ce." Ban bata komai ba wallahi."
Ya d'an Harare ni yana fad'in." To yaushe kuwa za ta saurari rarrashinki irin wannan ana had'awa da hasafi sai ki ga an shawo kan matsalar."
Na dinga gyada kaina ina dariya lallai ne kudi suna iya sayan komai amma ban da rai da rayuwa.
Miliyar biyar ya tura mata bai gaya mini ba amma yana tura mata da kamar minti goma ta kira ni a ki'dime har da rawar murya "Amina don girman Allah ki kara yi mini godiya yanzu nan na ga sa'ko 5m na gode na gode na gode Allah Ya saka da alheri ga sabon gida an ce za a ba ni."
Dariya ta kama ni na ce." Sahura yanzu don Allah ina rantse-rantsen da ki ka dinga yi, Idiris fa aure zai ka'ra ko kin manta."
Ta ja tsaki tana fad'in." Wallahi tallahi Amina saboda Yallabai ya saka ba ki a maganar nan zan koma zaman aure da Idiris amma wallahi ba don haka ba sai dai ya aiko mini da takardata."
Ta kashe wayar ba tare da ta jira ta ji abinda zan ce ba."
Ya dube ni yana fad'in." Ba ki kyauta ba Amina." Ina dariya sosai na ce." Don ba ka ji rantsuwar da ta dinga yi ba shine abinda ya ba ni dariya da mamaki."
Ya gyad'a kansa Shima da d'an murmushi a saman fuskarsa ya ce." Ai tace saboda na sanya ba ki zata koma. Kuma wallahi na ji dad'i sosai tuntuni na fahimci cewa ai tana da kirki da saukin hali."
A tak'aice na ce." Hakane kam Sahura mutum ce har da rabin mutum mun gode sosai ta ce na sake godiya ina yi akan kaina da ita Ubangiji Allah Ya sa kafi haka."
Ya amsa da Amin suma Amin yana kallona.
Na dan sauke ajiyar zuciya kafin na ce." Sai mu yi maganar Hauwa tunda mun sasanta wannan  auran."
Ya bata rai yana fad'in." Za ki bata mini rai kenan ko?"
Na ce." B'acin rai kamar yaya?"
Cikin 'kosawa ya ce." Maganar Hauwa ta ishe ni a gidan nan Amina, ya kamata ke ma ki bar ta kamar yadda na bar ta ba na son abinda zai rikita mini gida dama can itace husumiya yanzu da bata nan ba gashi kuna zaune kalau da Maryam ba."
Haka kawai sai na ji rashin jin dadin maganarsa. A ganina kamar Hauwa bata cancanci haka daga wurinsa ba duk da bai gaya mini abinda ya faru ba a wajan sulhunsu amma na lura haushinta da yake ji ya sake ninkuwa. Zaman da na yi da ita na fahimci macace mai taurin kai da girman kai har shi eanda ya ajiyeta yi masa take kuma a cikin ayyukan da ta dinga yi a gidan nan da gadara da iko take gudanar da komai dalili tana ganin kamar ta fi kowa dangantaka mai karfi bayan ta aure duka na fahimceta. To amma ni wannan baya damuna tunda nasan matsayina a zuciyar mijina ko bai fito ya fad'a ba. Ba na sha'awar a ce sun rabu gabad'aya ga zuria a tsakaninsu mai k'arfi kamata ya yi a ce sun sulhunta junansu sun yi hakuri sun cigaba da zama.
Ganin yadda ya had'e rai da nuna baya buk'atar sake maganar Hauwa sai na shigo da maganar zuwa maiduguri tunda shi ya yi mini alkawari ya ce za mu je a karshen wata amma daga mun dawo za mu tafi legos tunda Alhmdullhi jikin matar tasa ya yi sau'ki.

***
Abinda ya faru kenan kamar yadda ya yi mini al'kawari cikin karamci da kara da kulawa muka je maiduguri tare. Ya bi dangin Mamana da alheri mai yawa. Baban Saude bayan gari a lokacin da muke je garin. Da yawa wad'anda ba su ta'ba ganinsa a zahiri ba suka yi tozali da shi tare da alherinsa. Ni kuma na sayawa Fadila sabuwar freezer 'katuwa  da kenan d'inki domin yin sana'ar sayar da ruwa da 'kan'kara.
Kwananmu biyu kacal a maiduguri muka yi sallama da su.

A ranar da muka dawo a gidan Momi ya kwana washe gari ya shigo mini a hargitse yana gaya mini jikinta ne ya sake tashi jiya ba su yi wani baccin kirki ba suma ta yi sai gefan asubahi ta dawo.
Ya ba ni tausayi sosai itama haka domin da gaske ne duk mai zuciyar imani idan ya ga  halin da take ciki zuciyarsa sai ta motsa. Dole shiryin tafiyarmu Legos ya rushe yadda hankalinsa ya tashi da ciwon komai nasa tsayawa ya yi

Kwana biyu a tsakani ya sake kwasarta suka sake koma can kasar hindu din asibitin da suka kula da ita a wancan karon domin sake duba lafiyarta.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da

kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book complete 2k akan telegram normal What'sapp group 1k via 0542382124...binta Umar gtbank*
07084653262
Tun bayan tafiyarsu sau biyu muka yi magana dashi kamar dai wancan lokacin da suka tafi muna had'uwa ne ta What'sapp mu yi vidiyo call abinda ya kasance kenan amma wannan karon babu nisha'di da annashuwa a tare da shi muka yi magana. Idan na tambaye shi yanayin jikin nata sai ya ce mini da sauki. A wancan lokacin yi yayi kamar sabon angon da yake watayawa da amaryarsa ya yi fresh dashi don har na dinga tsokanarsa wannan karon kuwa akwai firgici da damuwa a tare da shi ko bai fad'a ba yanayinsa ya gama nunawa.
Na kasance cikin yanayi na tunani da zullumi domin yau tafiyarsu kwana goma sha daya kenan kuma a cikin kwanakin sau biyu kacal ya ta'bo ni, tun daga ranar ma ban sake ganinsa a WhatsApp din ba. Idan na kira waya ta yanke ko na ji busy. Gaskiya na damu sosai hakan ya sanya mini rashin nutsuwa domin sai zuciyata take ta yi mini sa'ke-sa'ken mugun abu bayan mafarkin da nake yi wai gani ina da dariya da ita mara lafiyar muna hira muna ta k'yalkyala dariya. Masana mafarki kuwa suna fad'in yin dariya a mafarki ba alheri ba ne.

Gaza ha'kuri na yi na sanar da Baba Tabawa halin da ake ciki itama ta taya ni zullumi tana ta addu'a Allah Ya sa lafiya ina amsawa da Amin.
Idar da sallar magribata kenan na d'auki wayata dake saman dirowa ba na iya minti ashirin yanzu ban bud'e data na duba ba. Cikin ikon Allah kamar iska sakonshi ya shigo. Hoton Momin ya turo mini cikin mawuyancin hali gabad'aya duk ta 'kare ta yi fiyat da ita tana kwance a tsakure a gado hancinta da abin taimakawa numfashi. Na tsorata ainun da ganinta duk da ba a zahiri ba ne hoto ne sai da na ji wani irin tashin hankali ya rintsa da ni a lokacin zuciyata ta karya na kasa jimirin jure danne hawayen da suke danno

mini. Suka fara sauka a kumatuna. Wannan ciwon ya gama cinye matar nan manya cutuka sun zagaye rayuwarta.
Vidiyo call ya kira ni ina goge hawaye na danna da ya ga ina kuka ya fara tambayar menene. Na ce." Ni dai daka sani ba ka turo mini hoton nan nata ba hankalina ya tashi wallahi."
Ya girgiza kansa yana fad'in." Tana jin jiki sosai Amina ku taya ta da addu'a gabad'aya bata gane wanda yake kanta numfashi kuwa sai da taimako."
Na goge hawayen da yake tsiyaya ina fad'in." Allah Ya saukaka mata. Kai kuma Allah Ya baka lada."
Ya furta da "Amin." A tak'aice kafin ya cigaba da cewa." Kwana biyu mun d'an yi rashin service a garin. Sai jiya da daddare  ya daidaita ban kuma samu sukunin ta'bo ki ba sai yanzu ina fatan kuna kafiya."
Na ce." Wallahi lafiya lau, ni ma ina nan hankalina a tashe gabad'aya na kasa nutsuwa ina ta tunanin halin da kuke ciki."
Ya d'an yi murmushi kafin ya kanne mini ido ya ce.'' Ni kuma mafarkin ki na dinga yi kullum na kwanta sai kin zo mini har na yi wanka da asuba."
D'an harararsa na yi na ce." Kai kam ka daina haka don Allah."
A sakarce ya ce." To ya za a yi ne Amina da gaske nake wallahi kin san kuwa ba zan yi miki rantsuwa akan son rai ba. Mafarki nake yi ina tara dake duk dare kuma na yi wanka." Na ce
"Allah Ya kyauta."
Ya amsa da "Amin.'' Kafin ya ce." Bari zan ta'bo ki kafin na kwanta sai mu yi hira ko?"
A sanyaye na ce." To." Ina mamakinsa duk yanayin alhinin da yake ciki halinsa na fitina yana nan.
Na ajiye waya tare da yin kasa'ke gabana sai ya buga da k'arfi idan na tuna halin da naga matar nan a ciki.
Wayar na d'auka na yi saurin goge hoton ba tare da na sake kuskuran sake gani ba.

To har na kwanta ban ga motsinsa ba. Da asuba kuwa ina gama ibada kamar koyaushe  na bud'e data sakon shi ya shigo kamar iska.
"Innalillahi  wa'ina ilaihi raji'un! dana fara gani tun kafin na bud'e sakon shine abinda ya assasa mini 'barin jiki da kakkarwar hannu. Na bude gabana na bugawa da karfin gaske...
_"Allah Ya yi wa Maryam rasuwa a daran nan ki sanar da duk wanda ya kamata Amina."_ Abinda yake rubuce kenan
Wani irin tsananin tashin hankali da d'imuwa na shiga ina daga zaune na dinga jin tafin kafata na wani irin yammm! hannuna da ke ri'ke da wayar ya sandare wayar ta fad'i saman cinyata.  Ni kaina saukar hawaye na ji a saman dakalin fuskata suna kasa tsare da babban sauti na furta." INNALILLAHI WA'INA ILAIHI RAJI'UN! Allah Ya jikanki Maryam, Ubangiji Ka yafe wa baiwarka, ashe ciwo ba na tashi ba ne."
Wani mahaukacin kuka mai gunji ya taho mini a guje! Na sanya tafin hannuna na toshe bakina ina fad'in." Mun shiga uku a wannan duniyar da bata da tabbas Ya Allah!!"

Wayar na laluba da saurin gaske tabbas wannan shi zai zama izna ga Hauwa ya nuna mata cewa babu abinda yake cikin wannan duniyar face rikici da firgici tashin hankali da rashin tabbas
Bugu d'aya wayar ta yi ta daga cikin kukan da na kasa jimirin danne shi na ce." Hauwa Momi ta rasu."
Cike da rikicewar murya ta furta." Wac...wace Momin kike nufi Amina?"
Yadda ta fad'i maganar shi ya tabbatar mini da cewar a ki'dime take... Na ce." Momi dai da kika sani matar mijinki Hajiya Maryam."
Dif ta yi sai sautin shuhhh! ne yake tashi a kunnana. Na daga wayar na duba tana ta tafiya. Sunanta na kira ta amsa a sanyaye "Na'am. Na ce." Ki sanar da inna Uwani halin da ake ciki Hauwa kin ga dai duniyar ko ita kenan fa."
Ta yi shiru dai bata tanka ba. Na ja ajiyar zuciya ina jin yadda wani kutittiran abu ya tokare mini a wuya ba komai ba ne face damuwa da tsananin kidima da tashin hankali.
Jin ta yi shiru ba ta ce komai ba sai kawai na datse kiran na nemi lambar Hajja domin ba na tsammanin ta san da rasuwar tunda a sa'kon da ya rubuto mini ya ce na gayawa wanda ya dace.
Sosai Hajja ta gigice da ta ji labarin rasuwar dan har sai da na yi dakacen sanar da ita tunda ita kanta ba ta da koshin lafiya. Kasa jimirin saururan kukanta na yi na datse kiran hannuna na rawa na ajiyeta saman cinyata hawayen suka sake zubo mini a saman fuska. Hannu nasa na sharce na sake saukar waya a karo na uku anti Yagana na kira na sanar da ita  domin ta gaya duk wanda ya dace a yi jana'iza da shi.  Na kira Babanmu na sanar dashi shi ma ya tabbatar mini da cewar za su kamo hanya gobe da sassafe shi da Baba Sule.
Jiki a sabule na fita falo baba Tabawa tana d'akinta sai na bita can. Na sameta tana ninke kayanta ganin yanayina ya sanya jikinta mutuwa. Rashin kwarin kafafuna ya sanya ni zubewa gabanta na furta." Baba Tabawa Momi ce ta rasu fa?"
"Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! Kalmar da ta fara furtawa kenan kafin ta tallafe ha'barta cikin alhini da tace." Baiwar Allah nan ashe ciwo ba na tashi ba ne." Hanci na ja tare da furta " Baba tunda ranar da muka je dubata farkon ciwon  Awallahi hankalina ya kasa kwanciya haka kawai daga ta fad'o mini sai gabana ya yanke ya fad'i wallahi ciwon nan nata ya tsaya mini a rai na sosai."
Ta girgiza kai cike da kasala ta ce." To a Amina abin ne da ban tsoro ga yanayin yadda hallittunta suka jirkice ba ke kad'ai ba ni kaina da ita nake kwana da ita nake tashi a rana wallahi  Ubangiji Allah Ya gafarta mata ya yafe mata, halinta nagari ya bita don arzikin Annabi."
Da "Amin na amsa tare da cigaba da nanata Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un domin samun nutsuwa da k'adaita Allah da kuma tabbatar da cewa gare shi muke kuma gare shi za mu koma.

Wannan littafin na kudi kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Mun jima muna alhini tare da tariyo kyawawan halinta ( mu kula anan kun san dai a al'ada koda mutum ya ninke (boye ) abinda ya shuka na sharri da rashin kyautawa a duniya babu yadda za a yi a ce rud'ani da razani na mutuwa ya bari mutane su iya furtawa. Ku sani ko kafiri ne ya mutu a matsayinka na musulmi kaga gawarsa sai ka shiga hankalinka lokacin ne za ka tuna lallai fa ni ma akwai wannan ranar za ta zo mini ba tare da na yi shiri ba. Zan mutu za kuma a haka rami a binne ni. Amma ita mutuwa ai mai tonan asiri ce idan an shuka kairan za ta nuna idan sharrin ma aka shuka duka zata nuna. Mu bi a sannu a hankali a daina yanke hukunci don Allah kuma a fahimci sa'kon da ake so a isar a wannan littafin ta kowace siga zai fita yadda kuke so)

Sahura na kira a waya na gaya mata. Itama dai kamar yadda yake faruwa a al'ada a kidema take fad'in." Da gaske ta rasu Amina?"
Na ce." An ta'ba wasa da mutuwa dama, wallahi ta rasu da gaske. " Ta dinga nanata kiran sunan Allah tana istigifari da fad'in Allah ka yafe mana.
Na ce." Mutuwar matar nan ta dake ni wallahi
Sahura ba ki ji yadda nake ji ba a raina na tsorata da wannan duniyar gabad'ayanta. Ita kanta Hauwa tana can cike da gigita domin kasa magana ta yi da na kira ta a waya na sanar da ita sai kashe wayata na yi domin bakinta ya mutu murus ta kasa magana."

"Ai Amina mutuwa wa'azi ci ga duk wanda Allah Ya sa zai hankalta, duk d'aukaka da sharafin mutum a duniya ba iya tsallaketa. Mu 'yan adam ai muna da mantuwa shiyasa muke ganin kamar ba za ta zo kanmu ba, a yadda dai kike ba ni labarin irin abinda Hauwa take yi wa matar nan wallahi ita ya fi kamata mutuwar ta dake ta, ta kuma ji tsoron Allah har ta mutu bata nemi afuwarta ba Allah baya yafe hakkin wani akan wani har sai wanda aka zalinta ya ce ya ya yafe, aikin banza ai kishi ba hauka ba ne, ni kaina Hauwa ta ba ni mamaki kuma na raina wayo da iliminta domin jalihi ne kadai ba zai fahimci cewa ba hassada take yi wa baiwar Allah nan ba, misali dani daku duka hasashe muke akanta domin ba mu da tabbas a duniya muke ji ana fad'in mashirika ce amma ai ba mu ta'ba ganinta tana yi ba. Idan ma tana yi din wannan ita da mahallicinta ne, ni yanzu tsoron duniyar nan nake yi wallahi Amina kowa ya kashe wutar gabansa."

Shiru na yi ina ta auna maganganun da take yi. Ni kaina na kan zauna na yi ta nazari akan mai yasa Hauwa ta zafafawa matar nan da yawa. Kishi ne ko hassada mai yasa komai sai ta mayar da shi rigima da sa'insa lefi ni aka yi wa amma ban yi irin abubuwan da take yi ba, tabbas dole a dora ayar tambaya a kanta koda kuwa ba hakan ba ne a zuciyarta ni kaina ba zan fita daga zargi ba tunda yan uwanta da yawa suna ganin cutar da ita muke yi ta hanyar hade mata kai da yi mata tawaye tare da fito da kishi muraran. Idan zan kwana ina rantsuwa da Allah kan cewa ba ni yi mata hassada da b'akinciki babu wanda zai yarda.

Haka dai muka yi sallama cikin yanayi na damuwa da tashin hankali.

Baban Saude ya kira ni yana tabbatar mini da cewa suna kan hanya suna da d'an yawa.
Na kira Babanmu ya ce mini shi ma sun taso su uku har da Ummansu Hadiza. Wanka na yi na kintsa na fita falo cikin hijabi har kasa na samu Baba Tabawa itama cikin hijabin da carbi ta kammala abin kari da d'an dama. Da asuba na ce ta yi abinci da yawa saboda bakin da suke tafe. Muka gaisa tare da sake yi wa juna gaisuwa. Masa'udu tare da
Sale suka  shigo da akwati kafin shigowar Hajjan Kamalu ne ya fara shigowa tukkuna suka shigo Hajja da Gwaggo da Hamusu a biye a bayansu.
Bakin kofar na isa da sauri ina yi musu barka da zuwa. Na kar'bi jakar dake hannun Hajja ina fad'in." Gwaggo sannunku da hanya Hajja kun yi sauri sosai fa kamar a hanya kuka kwana."
Suka zauna a kujera tana fad'in." Kina fad'in rasuwar na ce Kamalu ya sanar da Gwaggo maza ta shiryo mu taho
kuma dai Garba ya k'ure gudu sosai shiyasa  Allah Ya kawo mu."
Na nutsu sosai muka gaisa a tsanake Hamusu dake can saman kujera mai cin mutum d'aya ya gaishe ni na amsa tare da tambayar iyalinsa da yaronshi Arif da bai wuce shekara uku ba ya ce mini duk suna lafiya. Baba Tabawa bayan sun gaisa da yi wa juna ta'aziyya na ce ta kawo  musu abinci domin bayan karin kummalon da ta yi da yawa  har ta kammala na rana
Na dubi Kamalu dake gefe a tsaye jikin labule ya sake girma da fad'i sosai suffa ta mazantaka ta bayyana a tattare dashi har da gemu ya fara ajiyewa. Yatsansa makale da carbi mai lamba yana ta rarraba ido a kanmu yanayinsa gabad'aya kamar mai nazarin wani abu damuwa da tashin hankali sun gama bayyana a tattare dashi. Ganin mun had'a ido dashi ya sanya ni janye nawa idon. Ina jin wani abu na taso mini da tashin hankali. Kawai zuciyata ta fara raya mini cewa ni ma haka zan fadi na mutu yarana su sake kasancewa cikin maraici.
Ya gurfana a gabana cikin kula da ladabi ya furta."Mama ina kwana ya muka ji da  hakurin wannan rashi."
Na amsa da "Alhamdulillahi mun gode Allah."
Ya furta." Allah Ya jikan Momi Ya gafarta mata."
Gabad'aya muka amsa a falon.
Na dubi Hajja tare da fad'in." Yusi bai samu zuwa ba ne.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
□□□☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*

*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*PAID BOOK 2K COMPLETE ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1K VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
A tsanake ta ce." A a ai tare duk muke tafe tun a waje ya ce Garba ya ajiye shi yana can tare da Adamu."
Na gyada kaina ba tare da na sake cewa komai ba. Baba Tabawa ta kawo tire uku masu girma cike da abinci na taimaka mata wurin zubawa kowa Hajja ta ce ." Hajiya Saratu tana tafe in sha Allahu mun yi waya da Alhaji Sa'idu shi da d'an uwansa Alhaji Dahiru sun ce za su yi kokarin samun jana'iza."  'Yan uwan mahaifin maigidan ne wanda a yanzu su kadai ne suka rage musu a family din. Na gyada kaina a sanyaye na ce." Allah Ya kawo su lafiya.

Kai na jima ban shiga tashin hankali da nadamar rayuwa ba sai a rasuwar baiwar Allah nan. Tunda gawar ta iso gabad'aya estate din namu ya cika da motoci jama'a daga kowace kusurwa abokanan maigidan dama wasu daga ciki abokan tsohon mijinta ne. Cikin gidanta cike da 'yan uwanta da zuriarsu tare da abokanan arziki da yaranta masu yi mata hidima na shagunanta. Ana ta koke koke masu dauriyar daga ciki kad'ane. Babbar yarinyata Nusaiba sumanta biyu har yanzu ba ta gane wanda yake kanta ba. Nabila kuma tana ta iskokai a wani d'aki da 'yan uwansu sun kulle-kulle kofa don kada ta fito daga inda muke a zaune muna jin ihunta. Cikin masu yi wa Momi wankan gawa har da Baba Tabawa lallai na yaba k'warai da aniya wurin jajuecewarta da dauriyarta koda yake yadda take ba ni labari a gaban idonta mahaifiyarta ta rasu kuma itace ta wanke ta. Wannan ya kara tabbatar mini da cewa Baba Tabawa tana daya daga cikin salihan matan da Ubangiji ya ce lallai yana jin kunyarsu a gidan duniya da lahira dalilin rashin haihuwa.
Ban tashi tabbatar da cewa d'an adam ba a bakin komai yake ba sai da aka gama had'a Maryam tsaf cikin likkafani a mike cikin makara ta zama 'yar mitsitsiya a tsakiyar makarar tsabar ciwo ya cinyata
ana ta lallabata sunanta gabad'aya ya shafe daga jiya zuwa yau din wasu na kiran ta da gawa wasu na kiranta da marigayiya. Yaranta da mijinta tare da yan uwanta sun kewaye makarar yayin da masu aikinta mata da muke tare da su a gidan suke gefe sun cure kansu wuri d'aya sai shar'bar kuka suke yi. Adamu dake tare da Yusi ya can gefe daya kuka yake yi sosai yana fad'in." Momi kin mutu da wa ki ka bar mu a duniya, ba mu da uwa ba mu da uba. Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!.
Sambatun da yaron yake yi ya kidima ni sosai ya kuma ba ni tausayi ainun na yi saurin d'auke kaina daga kansu Yusi yana ta rirrike shi sun kasa zuwa gaban gawar ma gabad'aya.
Hajja da Gwaggo suka nufi bakin makarar. Na yi na yi na ja kafata domin bin bayansu na kasa don wata irin juwa da Hajijiya nake ji idona na ganinsu garagara,
Bayan haka kuma gabad'aya a tsarge nake ga yanayin kallon da na ga wata mata da na ji suna kiranta da suna Yabi take yi mini irin na wulakanci da neman fitina.
Hawaye masu d'umi suka silalo kumatuna wanda ya yi daidai da lokacin da na yi hu'bbasa wurin sarrafa 'kafafuna amma suka doje ban san yadda aka yi ba kawai na ji ni a k'asa na zube a lokacin ne kuma naga kamar gilmawar wani abu daga sannan ban sake gane komai ba sai dana farka tukkuna na tabbatar da cewar suma na yi lokacin har an kaita makwancinta an dawo. Anti Yagana sun iso tare da Inna Uwani. Ban yi mamakin ganin yanayinsu ba domin akwai d'imuwa da tashin hankali na rasuwar da aka kwantsama. Ko baka da ji'bi da mutum fad'in Annabi ne mutuwarsa dole ta nasheka balle wannan matar da alherinta kowa yake gani.
Hajja ta shigo d'akin da muke tana fad'in." To alhamdulillahi tunda ta tashi da ji da ganinta da kuma lafiya mun gode Allah Yagana taimaka mata sai mu

koma can gidan nasu mu yi namu zaman domin nan din zaman zai zame mana fitina.
Gwaggo da fitowarta daga bandaki kenan d'aure da alwala ta ce." Ni ma shawarar da na yanke kenan hakan zai fi alheri."
Anti Yagana ta dube ni a d'an sanyaye kafin ta ce." Sannu ba dai kya jin komai a jikinki ko?"
Kaina na gyad'a mata a nutse na ce." Ashe kun zo?"
Ta ce." Mun zo mun tarar an d'auki gawar gidan a kacame ana ta hayaniya ke kuma gaki a sheme sai da likitanku ta zo ta dubaki fa dogon suma ki ka yi."
Shiru na yi ina nazarin maganarta kafin na ce." Anti Yagana mai ya faru ne?"
Ta'be bakinta ta yi ba ce mini komai ba. Na daga kaina na kalli Hajja dake tsaye jikin bango rumgume da hannunta a k'irji nan take na karanci damuwa da b'acin rai a saman fuskata.
Ban sake wata magana ba na tashi zaune hijabi na da yake gefe anti Yagana ta miko mini na zura a jikina tana taimaka mini na yun'kura na tashi ta ri'ke ni. Na ce." Ki cika ni zan iya tafiya da kafafuna. Inna Uwani ta ce." Da dai kin bari ta rike ki jikin naki ai har yanzu bai gama daidaita ba.
Hajja da Gwaggo suka yi gaba.
Wani irin kallo dangin marigayiyar suke mini na tsana da kyama. Anti Yagana ta juyar da kanta ba ta ce komai ba. Ni ma ban ce musu komai ba na ji ita wannan matar mai suna Yabi tana fad'in." Kun kai ta kasa kun ji dad'i, sai ku jirayi hakki domin wallahi ba mu yafe muku ba, duk abinda za ki nuna a banza a wofi Maryam dai karshenta ya yi kyau ku kam in sha Allahu mutuwar wulakanci za ku yi."
Maganganunta ne suka dinga yi mini amsa kuwawa! a kunne gabana ya dinga bugawa da karfi da karfi. Wannan babban kalubalen ban shirya tararsa ba a yanzu domin ba ni da hujjar da zan kare kaina Allah shine shahidi.
Muka fita tun daga haraba cike da jama'a har zuwa waje mutane cike cikin manya manyan rumfunan da aka kafa.
Kafafuna suka dinga hard'ewa gabad'aya sai na tsargu domin maganganun da matar nan ta yi sun sake dakusar da duk wani karsashi da kwarin gwiwata. Shin wane irin kallo jama'a suke yi mini a yanzu dana fito cikinsu. Cikin dubara na janyo saman hijabina na rufe fuskata dashi dama rike nake a hannun anti Yagana. Ina jin sanda Hajja ta tsaya suna gaisawa da ire-iren abokanan Yallabai din na ce da anti Yagana ta yi sauri mu wuce domin ba ni da wani k'umaji da nutsuwar da zan iya tsayuwa a gaban jama'a domin kar'bar ta'azziya. Muka yi gaba muka bar su ita da Gwaggo suna gaisawa.
K'uryar d'akina anti Yagana ta dangane da ni na zauna kan gado kamar wata sabuwar amarya na yaye hijabin da ya katange fuskata. Muka had'a Ido nan take na rushe da kuka na ri'ke hannunta katamau! Jikina na kyarma na furta." Anti Yagana Hajiya Maryam ta mutu sanadiyar lalure-laluren da suka yi mata hijabi, ina tsoron kada 'yan uwanta da jama'a su jinginta rasuwarta da ni da Hauwa, ai kin ji abinda daya daga cikin 'yan uwanta take fad'a ko?"

" 'Karamin tsaki ta yi kafin ta ce."Amina duk wanda zai alak'anta rasuwar matar nan daku to dama can ba masoyinta ba ne. Su kansu 'yan uwan nata da suke ko'karin tashin husuma ba kaunarta suke yi ba tunda har suke jingina rasuwarta da wani abu daban. Kishi halak ne kuma duk gidan da aka had'a mace fiye da biyu ana samun irin wad'annan matsaltsalun. A ganina wannan ba wani abun damuwa ba ne, rigima ce suke nema kuma in sha Allah rabbi har a share makoki ba za mu tanka musu ba. Ni gidan ma ba zan sake shiga ba tunda na lura duk yawansu babu mai dattako a cikinsu. Rashi kam ba su kadai suka yi ba mutane da yawa ne domin Hajiya Maryam bango ce majingina kuma uwar marayu har ma da masu uban. Don haka iyakacin k'aunar da za su nuna mata su bita da addu'a tare da rungumar abinda ta bari shine kawai sakamakon da za su yi mata bayan rayuwarta. Don haka ki samu nutsuwa ki kuma daina tunanin kina da hannu lokacinta ne kawai ya yi kuma babu wanda ya isa ya tsalle rana da sa'in komawarsa ga Allah."

Maganganun anti Yagana sun d'an sanya ni mini nutsuwa kad'an amma har yanzu zuciyata ba ta daina yin tsalle akan abinda na ji yana fitowa daga bakin 'yar uwar marigayiyar ba.

Babanmu suka iso tare da baba Sule da Ummansu Hadiza kamar yadda ya fad'a. Baban Saude ne har yanzu bai shigo inda nake ba, anti Yagana kuma ta gaya mini tare suke da Babansu Fadila har da Baba Madu wanda ya kasance babban yayansu Mamanmu, mahaifin Babandi.

Kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Sai wajan biyar saura tukkuna suka shigo da d'an yawansu duk muna zaune a babban falo. Maigidan tare da iyayenshi biyu 'yan uwan mahaifinsa da kuma Baban Saude Baba Madu da Babansu Fadila. Falon ya cika da sabuwar gaisuwa tare da yi wa juna ta'aziya. Ta mussaman suka yi mini gaisuwar na amsa yayin da nake jin cikowar ruwan hawaye idona. Ina jin Hajja tana tambayar Alhaji Sa'idu Hajiya saratu ya ce tana can gidan mai rasuwar tunda koda suka sauka nan ta shiga ba ta fito ba kuma har yanzu. Suna ta tattauna hirar marigayiyar yayin da maigidan ke sake basu labarin irin wahalar da ta sha na jinyya farkon zuwansu asibitin a yayin da aka dora ta akan magani an ga sauyi sosai yanayin yadda yake magana da alhini shi yake nuna mutuwar ta dake shi kwarai da gaske kwarmin idonsa ya zurma fatar lebanshi ta bushe kamar wanda ya yi azimin shekara bai sha ruwa ba. Irin wannan yanayin ya shiga a lokacin rasuwar tsohon mijinta Alhaji Amadu da kyar ya dinga cin abinci. Yanzu ma ba na raba daya da biyu rabonsa da abinci tun da aka yi rasuwar kwana da yini kenan.
Gabad'aya sun jajanta sosai kuma kafin tafiyarsu sai da Baban Saude ya jagorancemu gabad'aya muka yi mata doguwar addu'a wadda take d'auke da surorin da ake karantawa mamaci. Yamma likis suka yi mana sallama gabad'ayansu har da Hamusu da Babanmu domin cewa ya yi shi ma ba zai zauna ba tafiya za su yi tunda sun yi abinda ya kawo su. Shi kansa maigidan

ya so su kwana ko daya ne amma gabad'aya suka ki har da kawunan nasa. Hajiya saratu ce kawai ta zauna ta ce sai an yi sadakar ukku tukkuna.
Yallabai din ya bada umarnin mayar dasu Babanmu gida. su Baban Saude kuma dama a motarsa suke tafe. Sai bayan sun tafi tukkuna Hajja ta dinga fad'a wai mai yasa anti Yagana ba ta jagoranci Ummansu Hadiza zuwa gidan mai rasuwar ba.
Anti Yagana ta ce mata mantawa ta yi shiyasa ni kuma nasan ba haka ba ne ita da kanta ta gaya mini k'afarta ba zata sake taka gidan ba. Gaisuwar da ta yi wa maigidan ma ta isa ba sai ta je ta yi wa 'yan uwanta ba tunda dukkaninsu taron tsintsinya ba share ne.
Sai bayan magariba Hajiya Saratu ta shigo. Ina d'aki lokacin na idar da sallah ban ka ga tashi daga kan daddauma ba ta shigo.
Na saki fuskata sosai Ina fad'in." Mai sunan Mamana ina yini?"
Ta zauna gefan gadona a nutse tana fad'in." Lafiya lau Yayata kuma diyata."
Na yi murmushi a hankali na ce." Ai tun d'azu aka ce kina can gidan marigiyar ina nan ina ta zuba idon ganin Mamana"
Ta dafa kafadata tana fad'in." Ga ni na shigo ai Amina ya muka ji da hakurin Maryam lokaci ya yi Ubangiji Allah Ya gafarta."
Na amsa da "Amin Ya Allah." Cikin wata iriyar murya.
D'akin ya d'an yi shiru wanda ya yi daidai da lokacin da anti Yagana ta fito daga bandaki daure da alwala. Ta saki fuska tana fad'in." Hajiya kin shigo kenan?"
Ta ce." E wallahi Yagana ya gida ya yaran, ya muka ji da hakuri?"
Anti Yagana ta ce." Ha'kuri da godiya Hajiya Allah dai ya jikinta da rahama."
Da Amin ta amsa yayin da take sake dora hannunta a kafad'ata.
Anti Yagana ta d'auki daddauma da hijabi ta koma can gefe domin gabatar da sallar magriba.
Ta ce." Ai ni ban fito ba daga gidan ba sai da na gabatar da sallata tukkun." Na yi murmushi kad'an ban ce komai ba.
Sai ta ce." Amina akwai maganganun da nake so mu tattauna dake idan babu damuwa."
Cikin nutsuwa na ce." Babu damuwa Hajiya Ina saurararanki."
Ta sauke ajiyar zuciya a tsanake ta ce." Duk abubuwan da suke faruwa a zamantakewar gidan nan ina da labari. Da har Ina cewa tunda matsalar ta'ki ta'ki cinyewa zan wanko kafata takasan na zo naji komai daga gare ki nasan ke ba za ki yi mini karya ba, ba kuma za ki goyu da bayan mijinki ko ki goyu da bayan Hauwa ba, idan har kema kina da lefi za ki gaya mini gaskiya sanin da na yi miki tun farkon fari.
Ta nisa kafin ta cigaba da cewa. Sai gashi kuma
rasuwar Hajiya Maryam ta ratsa hakan sai ya kara ba ni k'warin gwiwar zuwa domin na ji komai daga gare ki, Amina da hankalinki za ki biyewa Hauwa da har yanzu ba ta san rayuwa ba, mai yasa kuka kasa bawa mijinku k'warin gwiwa da taimako wurin ganin ya rike amanar abokinsa. Jimawata gidan marigayiya Maryam tana da dalili domin 'yan uwanta ne suka zaunar da ni suna wassafa mini irin zaman da kuka yi da ita da irin abubuwan da kuka dinga yi mata na rashin kyautatawa, idan har hakan gaskiya ne Amina ban

tsammata daga wurinki ba domin kallon da nake yi miki kin wuce a ce a yanzu an zauna a nuna miki abinda ya dace idan Hauwa ta yi hakan ba zan yi jayayya ba dama na san halinta da na ji sunanki a ciki ne  sai hakan bai yi mini dadi ba, mai ake gudu ne a zaman tare irin wannan fa, yanzu ina Maryam din take ta mutu ta bar duniya to mai zai sanya ba za mu yi hakuri da rayuwa ba. Gashi Hauwa har sai da ta yi sanadin da Tajo ya saketa saboda kuma bata da hankali ta tafi ta bar yaro jinjiri fisabillahi ina hankali da tunaninku yake?"
A nutse na dubeta tare da cewa." Mamana abubuwan da yawa sun faru masu dadi da akasin haka. Amma zan gaya miki wani abu da ba kowa ya san shi ba sai ni sai Ubangijin da ya hallice ni wallahi tallahi ban ta'ba kin Maryam a cikin raina ba. Tabbas akwai kishi kuma kowace mace tana da nata daidai gwargwado amma ni Amina ban zafafa shi akan matar nan ba duk sanda zuciyata za ta kitsa mini mummunan abu akan kanta nakan yi tirr da ita da take bijiro mini mugun nufi akan matar da alherinta ya fara riskata kafin wata mu'amula mai karfi ta ratsa tsakaninmu. Duk abubuwan da suka dinga faruwa yaranmu suka had'a amma ni da ita sa'insa mai muni bata ta'ba hadamu ba, kuma lafiya lau muka yi sallama da juna har ta koma ga Ubangijin talikai. Har yau har gobe ban k'ulleceta ba ban kuma k'ullaci yaranta ba ina jin tausayinsu kuma ina yi musu kallo irin na uwa." D'akin ya shiru bayan ajiye maganata na ja numfashi cikin bushewar ma'kogwaro na cigaba da cewa." Magana akan Hauwa kuma ni ba zan iya ce miki komai ba, abinda dai na sani shine Hauwa ta yi mini kokari kwarai  kuma babu kishi da ganin kyashin juna a tsakanina da ita ni fa a tunanina kenan, domin Hauwa 'yar uwa na dauketa ba kishiya ba. Duk hanyoyin na bi domin na nuna mata abubuwan da take ba su da kyau na bi, na yi bakin kokarina amma ba ta ji ba. Dalilin rigimarsu da maigidan tana da ala'ka da ni da ita mai rasuwar da yaranta. Mun daidaita a wattanin baya har na so ni da ita mu je mu dubata a lokacin da ta kwanta a asibiti amma fafur ta'ki sai tare da Baba Tabawa na tafi mai aikinm kenan. Wannan shine abinda zan iya gaya miki Mamana bayan hakan ban san abinda yake tsakanin Hauwa da mijinta ba tunda tun kafin ta aikata haka na yi iyakacin bakin kokarina a kansu ita dashi amma babu wanda ya saurareni a cikinsu."
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*

https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai

magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*
*2k COMPLETE ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1K VIA 0542382124.... BINTA UMAR GTBANK.*
*07084653262*

Ta jima sosai kafin ta yi magana cikin yanayi na damuwa ta ce." Dangin matar nan dai a ciki suke da ku Amina domin gani suke yi bakincikinku ne ya kashe musu 'yar uwarsu duk wanda ya zauna ya tashi sai sun amayar masa da abinda yake cikinsu.
Anti Yagana ta ja tsaki tana fad'in." To, abinda ya fi sai kawai su d'auki lasifika su fara bi sa'ko da loko suna shela tunda ba su da hankali, wannan ba k'auna ba ce abinda suke nunawa tsantsar jahilci ne kuma za su hana yar uwarsu kwanciyar lafiya a kabarinta muddin suka ce za su tashi rigima abubuwa da yawa ne za su faru. Dama zaman tare ai ya gaji haka dole a samu matsaltsalu ma bambamta sai dai kawai Allah Ya kyauta, ta wace hanya kike ganin za su hade mata kai ko su ware ta. Matar da ta samu soyayyar miji fiye da su, Hajiya Saratu ki duba maganar nan don Allah kaf fa yaransu suna hannunta basu da iko akan komai kina kwance kina jina Allah Ya jikanki, idan sun yi magana akan nuna rashin yarda ya goyu da bayanta. Ai ma sun yi

hakuri da ita wallahi kuma son su ta da zaman lafiya domin da wahala a ce wata uwa an yi mata fin karfin a kan yaranta ta iya dannewa sun yi namijin kokari anan kuma na yana musu. Mu dama tsakaninmu da ita alheri ne, wallahi koyaushe Amina ta gaya mini halin da take ciki na damuwa akan zamantakewar gidanta akan tausheta tare da nuna mata cewa haka auran yake gabad'ayansa jarabawa ce a ciki jin dadinsa kad'an ne kuma ibada ne, kokarinmu ta yi hakuri ta zauna a yau ba wai don yar uwata ba ce ina yabonta sosai dalilin abubuwa da yawa da ta dinga cin karo na b'akinciki da b'acin rai amma ta yi hakuri ta jure. Don haka idan 'yan uwan Maryam sun zargi Amina da Hauwa wajen gumawa Maryam takaici har ta rasu to sun so kansu kuma zahiri ba su bukataci zaman lafiya ba domin dai duk mai hankali ya san matar nan ta sha jinyya kafin ta rasu. "

Ta girgiza kanta tana fad'in." Hakane amma Yagana daidai ne Hauwa ta ajiye jariri sabuwar haihuwa ta shilla wata duniya ko a waje Tajo ya je ya auri yarinyar nan ya kamata ta aikata mana wannan rashin mutuncin. Jininmu ce fa ciki daya fa ba wasa ba ne Hakan ne ma ya sanya duk muka ture komai da jin zafin abinda ta yi Hajja ta ce mu je a bata ha'kuri bisa bin umarinta muke je can bauchi Hauwa ta rufe idonta ta yi mini dibar albarka zagi na ne kawai ba ta yi ba, hakan ya sanya na yi alkawarin cewa muddin da yawuna da shawarata Tajo ya gama zama da ita har abada tunda ta za'bi ta tozartamu shikkenan sai dai zumuncin ya lalace ."
Anti Yagana ta ce." A a ba za a yi haka ba Hajiya, ai ko babu dangantaka ta jini an riga an zama daya tunda har yara suka ratsa tsakani. Don kyautawa Hauwa ba ta kyauta ba. A dai nuna mata kuskuran abinda ta yi a gyara ta dawo dakinta a ganina shine abinda ya fi dacewa."
Ta gyada kanta ba tace komai ba tabbacin maganar anti Yagana ba ta gamsar da ita ba.
Na ce." Anti Yagana idan Hauwa tana da lefi shima yana da lefi fa. Domin ya yi abubuwa sosai wanda ya kamata a ce ya gane kuskure ne a zamantakewa amma bai gane ba, ni na yi kokarin dannewa dalili nasan babu wani abun da yake dawwama sai ikon Allah wanda shi muka gani yanzu. Na yi ta ko'karin bata shawara kan cewa ta kawar da kanta ta kasa jimirin yin hakan har sai da bacin rai ya ratsa tsakaninsu. Ya kamata gaskiya a tsage Mamana. Shi kansa maigidan akwai tashi matsalar sai dai ace ta Hauwa ta rinjayi tasa."
Ta ce." Ni dai da yawuna ba zan bashi umarnin dawo da ita ba duk hukuncin da ya yanke daidai ne."
Tana fad'in haka ta tashi tana cewa." Zan je na watsa ruwa can wurin su Hajja jikina duk ciwo yake yi mini na samu nasa wani abu a cikina."
Na ce." To shikkenan Mamana dama na ce da Baba Tabawa ta tu'ka mana towo don zai fi manà dadin ci akan tsabar shinkafar nan."
Ta ce."Aikuwa kin yi shawara mai kyau Amina don tunda aka sanar da ni rasuwar nan wallahi ko na sanya abinci a gabana sai dai na kalle shi ba na iya ci. Kai rasuwar baiwar Allah nan ta ta'ba ni wallahi."
Anti Yagana ta ce." Ba ke kadai ba wallahi ni kaina na gigita kwarai da aniya Ubangiji Allah Ya yi mata rahama."

Muka amsa da amin gabad'ayanmu kafin ta yi mana sallama ta fita daga d'akin, anti Yagana ta dube ni tana fad'in." Na so na tambayi Ummansu Hadiza labarinta amma na sha'afa wallahi, kuma don dai Babanmu ya ce sai sun tafi amma da ko kwana daya sai su yi tunda yanzu dole ne su kwana a hanya
ina so mu sake samun lokoci mu je mu sake dubata ko ya ki ka ce."
Na ce." Hakane anti Yagana ni kaina Hadiza tana raina wallahi, dalilin da ya sanya kenan na ce da Hamusu duk k'arshen wata ya dinga yi mata siyayya yana kai mata, zuwan namu yana da amfani ai hannunka baya rubewa ka yanke ka yar."
Ta furta." Ni har fargabar ganinta nake yi wallahi saboda ina tuna irin kukan da ta dinga shirga a ranar da muke je kin san da kyar aka tura ciki muka fito, na jima ina kukan zucci duk sanda na tuna da halin da take ciki nakan shiga yanayi na damuwa mace a irin wannan wurin a ajiye Amina duniyar nan ta baci duk da ba ita kadai ba ce, amma su kansu ma'aikatan wurin wallahi wasu daga ciki ba su tsoron Allah."
Cike da damuwa na ce." Anti Yagana lefin Hadiza na kisa ne ta kuma tabbatarwa da kotu gaskiyarta ba mu da wani yun'kuri da zamu yi domin ceto ta. Hakkin rai ba abin banza ne. Idan Allah Ya kar'bi tubanta kuma tana da ragowar rayuwa sai ki ga ta fito ta hanyar da ba mu yi tsammani ba. Idan kuma sun kasheta shikkenan sai ta riski Ubangijinta a wankakkiya. Ubangiji Allah Ya kare mu daga fadawa jarabawa da mummunar kaddara."
Ta amsa da Amin Ya Allah da yanayi na damuwa da nadama.

Misalin goma da rabi maigidan ya shigo tare suke da Kamalu ban yi mamakin ganinsu su biyu babu Yusi ba domin sai na ce ganina da Yusi daya kafin a d'auki gawar marigayiyar na hange shi tare da Adam a rakube a bayan kujera yana rarrashisa yanzu ma su Hajja da Gwaggo sai tambayarsa suke yi ina jin Kamalu na basu amsa da cewa yana can tare da Adam. Maigidan bai tsaya ba suna gaisawa ya haye sama hankalina gabad'aya yana kansa don haka ban yi jinkirin bin bayansa ba.
Na same shi zai shiga wanka da babban towel a jikinsa.
Muka zubawa juna ido. Na isa dab da shi na tsaye a sanyaye na ce." Ya karin hakuri tun d'azu nake ta so na yi maka gaisuwa ban samu dama ba, Ubangiji Allah Ya gafarta mata, kai kuma Allah Ya baka hakurin jure rashinta, Allah Ya albarkaci abinda ta bari."
Ya dinga amsa da "Amin Ya Allah cikin jin dadi. Ya nufi bandakin na bi bayan shi na taimaka masa wurin had'a ruwan wanka. Kallo yake ta bi na dashi babu yabo babu fallasa, amma kallon ya fara sa'bata sai na tsargu na fara tunanin ko shima ya fara yarda da abinda 'yan uwanta suke fad'a akanmu wato da bakincikinmu ta rasu. Da na tuna kallon nasa babu harara da k'yama a ciki sai na d'an samu sassauci, na fito na bar shi a bandakin domin ya yi wankan. Na zauna jigum cikin zullumi.
Ya fito yana tsane jikinsa na tashi da sauri na bude wardrobe dinshi jallabiya na fito masa da ita da gajeran wando. Na mika masa ya kar'ba na koma na zauna yana kintsa jikinsa ya ce." Ki kawo mini abinci Amina."

Da sauri na mike ina fadin." Dama abinda zan tambayeka kenan, tun yamma na ce da Baba Tabawa ta yi towo zai fi dadin tafiya."
A takaice ya ce." Kin kyauta kuwa."
Ya d'auki turare yana fesawa a jikinsa. Na sauka kasa cikin nazarin abinda ya yi a ganina wane turare zai fesa a cikin wannan yanayin da matarsa ta rasu ko kwana daya ba ta yi a kabarinta ba
Na koma saman da tire a hannuna mai d'auke da kwanonin abincin da duk abinda nasan zai buk'ata. Yana zaune gefan gado
yana waya da Sukairaju na ajiye tiren hannuna a saman daddumar da yake zama domin cin abinci...

Ina binki bashi idan kin san kina karanta littafin nan ba ki biya ni hakkina ba.

Sai da ya kammala wayar tsaf tukkuna ya zo ya zauna saman daddumar da abincin yake a shirye. Na zuba masa guda biyu madaidaita ina ko'karin zuba miya ya furta." Wanene zai cinye miki wannan towon Amina?"
Na dube shi a tsanake kafin na ce." Kai ne za ka cinye?" Sai ya gyada kansa yana fad'in." A a d'aya ya ishe ni, kada ki zuba miya a kai a b'ata shi ki yi addu'a d'ayan ma na iya cinye shi."
Ban ce komai ba na cire dayan na mayar cikin fulas na fara ko'karin zuba miyar ya ce ki zuba ta yau'kin kawai kada ki sanya mini jar miyar, ki sanya mini man shanu akai wadatacce."
Na yi yadda ya umarta Ina fad'in." To naman fa." Ya ce." Ki tsamo sai ki sanya mini."
Ban ce komai na dinga tsamo naman ina zuba masa a saman towon har ya so yayi yawa." A nutse ya ce." Naman nan ya isa haka Amina, kina so na ci abinci jikina ya mutu ko?"
Na girgiza kai a hankali na ce." Kallo d'aya na yi maka d'azu na tabbatar da cewa akwai yunwa a tattare da kai wallahi."
Ya furta." Ba ki yi karya ba rabona da abinci tun yammacin jiya kuma ban wani damu ba wallahi."
A nutse na ce." To yanzu dai ka daure ka cinye wannan har naman duka."
Hannunsa ya sanya tare da bismillahi kafin ya ce." To ke ma sanya hannunki mu ci tare zai fi albarka.
Na sanya hannuna a hankali na gutsiro na kai daidai bakinsa.
Kallona ya yi na 'yan sakkoni kafin ya bud'e bakin na sanya masa towon ya fara taunawa a tsanake
D'akin ya d'auki shiru na wani lokaci kafin na ji maganarsa yana fad'in." Ina mai sunan abokina ya 'kara wayo ko.?"
Na ce." Ya yi wayo sosai su Hajja ma suka dinga mamaki girman da jikinsa ya yi suna fad'in kamar yana sha nono saboda jikinsa ya ginu babu motsewa ko wata matsalar gaskiya yana samun kulawa sosai a wurin Baba Tabawa ba shi da matsalar maraicin nonon mamansa."
Da d'an jin dadi ya ce." Na gode Allah na kuma gode muku Amina ina mutukar godiya Allah Ya saka muku da alheri

'Dan tausayi ya ba ni domin yanayin yadda ya yi maganar ya nuna mini cewa har yanzu yana jin zafin abinda Hauwa ta yi kuma abin ya dame shi abubuwa ne da yawa suka yi masa dabaibayi. Ta bakin Hajiya Saratun Hauwa ko a waje ya aurota bai kamata ta yi wannan sakarcin ba. yaro
d'anyar haihuwa ta ajiye saboda wani banzan dalili.
Na ce." Ni kam banga abin godiya ba duk abinda na yi maka ai kaina na yi wa."
Ya yi shiru bai ce komai ba yana dai ta kar'bar towon da nake bashi a baki har guda ya kusa k'arewa ya ce." Ban ga kin ci ba."
"Na ce." Sai ka koshi my love dina." Ya sa dariya wadda ban yi tsammani ba yana fad'in." Na ga sai wani ji ki ke da ni Amina."
Da d'an murmushi na ce." Tausayi ka ba ni." Ya gyad'a kansa da wani irin murmushi kwantacce a a tare dashi ya cinye malmalar towo daya na kara cire wani daga leda na cigaba da bashi bai hana ni ba. Jefi jefi muna d'an ta'ba hira mafi rinjaye kan marigayiyar ne. Da kyar na daure na soko maganar da take ta damuna na ce." Akan maganar da yan'uwanta suke yi akan mu ni da Hauwa wata'kila sun gaya maka kai ma ko?"
Ya ce." Wace magana ce kuma?"
Cike da damuwa na furta." Wai duk wanda ya shiga gidan domin yi musu ta'aziyya sai sun gaya masa irin zaman da muke da ita har suna fad'in bakincikin da muka jima muna guma mata ne ya yi sanadiyar rasuwarta."
Ya yi jim Yana kallona kafin ya ja siririn tsaki ya ce." Ke waye ya gaya miki haka?"
Kai tsaye na Mamana ce?" Ya san dama ina kiran yayarsa da sunan.
Sai ya girgiza kansa yana fad'in. " Mata dai ba a raba ku da k'ananun maganganu da fitina baiwar Allah ga sanadin mutuwarsa amma an jingina da wani lamari domin tayar da husuma ba ni so na ji bakinki a ciki wannan maganar duk abinda za su yi kada ki biye musu ku daga mini hankali don Allah domin na lura basu da kintsi dukkaninsu taron sakarkaru ne me yasa ga gaskiya 'kiri-'kiri a take gabad'aya da ni da su da ke mun san yadda ciwuka suka cinye Maryam har ajalinta ya sauka to me ya kawo wannan maganar kuma?"
Na ce." Ni ma abinda na gani kenan, kasan kuma dole ne na damu tunda ni ce a gidan yanzu, a ganina idan wasu basu yarda ba wasu za su yarda tunda Allah ne kadai ya san irin abinda suke fad'a a kanmu."
Ya ce." To kada wannan ya dame ki, tunda har maganar ta dawo kunnena zan yi wa tufkar hanci, na gaya miki dai kada ki kula su ku zubar mini da mutunci a gari."
A tak'aice na ce." In sha Allahu rabbi."

D'akin ya sake daukar shiru na wani lokaci kafin na sake yin kundubalar yin magana abin kamar wadda Hauwa ta sammace idan ma nace ba zan sake yin magana ba sai na kasa jurewa gabad'aya idan na tuna bata gidan sai na ji gabana ya buga kuma a raina sai nake ganin ai lefinta bai kai ace an rabu

da ita gabad'aya ba tunda shima ai yanayi mata lefi me yasa shi da yayarsa suka fi bata rashin gaskiya.

Na ce." Don Allah tunda haka ta faru ku yi hakuri Hauwa...... Ban kai ga kàrasa abinda yake bakina ba ya katse ni da babban sauti." Amina." Ya kira sunana na amsa da "Na'am tare da zuba masa ido gabana na d'an fad'uwa ganin yadda ya yi bala'in shan kunu......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*

*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book complete 2k ne a telegram what'sapp Gruop Kuma 1k via 0542382124.... Binta Umar gtbank.*
*07084653262*
*119*
"Na sha gaya miki cewar abinda yake tsakani na da Hauwa ba huruminki ba ne. Ko kuma lokacin da zan aureta na yi shawara dake ne? me yasa ki ke so k'ara mini damuwa akan wadda nake ciki, za mu samu matsala dake akan hakan ki kiyaye ba ni son maganar Hauwa a gidan nan daga yau."
Da k'yar na ce." To shikkenan dama gani nay.... Ya sake daga mini hannu yana fad'in ." Menene lefina Amina ko kema kina so ki nuna mini abinda ta yi ba komai ba ne? ina k'ara gaya miki ni fa Samira na ce ina so ba Hauwa ba, zan gaya miki wata magana wadda ba ki santa ba har yau na kasa mantawa da matata ta fari Allah Ya jikanta domin soyayyar gaskiya ce a tsakaninmu. Ban ta'ba kallon Hauwa a madadin da za ta share mini kukan rashin Samira ba, kuma ban ta'ba yi mata kwatankwancin son da nake yi wa Samira ba. Idan na rabu da ita babu wata tangard'a da zan samu tunda ni nasan bata da wani gurbi mai girma a zuciyata don haka maganar Hauwa ta kare a gidan nan na gaya miki Amina"

Duk yadda na so ganin na daure zuciyata daga barin jin zafin yadda yake yabon matarsa ta fari data mutu kasawa na yi sai na manta ma da maganar da muke tattaunwaa akai zuciyata ta fara tsalle tana tu'kuki tsabar zafin kishin  da ya taso mini na ce." Maganar Hauwa kuwa ba zata 'kare ba bari na gaya maka. Itace uwar yaranka uku, ai k'aryar so ta 'kare kuma ko kana sonta ko baka sonta ya zame maka tilas ka kalleta a matsayin wata jigo da ta samar maka da wani ginshiki da ka jima kana nema
wannan maganar da kake  furtawa kamar gugar zana kake yi mana ni da ita Hauwan kawai ka fito fili ka gaya mini cewa Amina har yanzu ban samu madadin Samira ba, ai ta riga ta mutu kuma duk wanda ya riga ya tafi baya dawowa sai kawai ka ro'ki Allah Ya takaita maka kwana ka je ka risketa a can ku gina sabuwar rayuwar da za ka wanzu cikin farinciki."
Ya zuba mini idonsa yana kallona. Na juyar da kaina gefe tare da sake had'e fuskata. Shiru d'akin ya d'auka bai ba ni amsa ba. Na tsame hannuna daga cikin abincin da nake bashi na  ya gi tissue paper domin goge hannuna. A hankali ya ce." Ban k'oshi ba."
Zumbura baki na yi na yun'kura na tashi tsaye sai ya riko hannuna tare da janyo ni jikinshi ya mike k'afafunsa na zauna saman cinyarsa. D'auke kaina na yi domin ji na yi ma sam bana son kallonsa saboda takaici wannan a cin fuska ne a takaice, haka kawai daga bada shawara.
Ya ce." Amina kalle ni."

Kallonsa na yi babu fara'a. Ya rintse idonsa a tsanake ya ce." Kin san jini a jikin d'an adam ko?"
Na yi shiru ban tanka ba. Ya d'an matse ni a jikinshi yana sakin ajiyar zuciya cikin kunnena ya furta." A jinin jikina kike yawo. Ina can wata uwa duniya kina yi mini gizo Amina ina alkawarin soyayyar da ki ka ce za mu yi idan na dawo gida?"
Da mamaki mai yawa a tare da ni na kura masa Ido. Ya sake matse ni a jikinsa yana me sanya fuskarsa tsakankanin wuyana wurin da yake bala'in so kenan a jikina.
Jikina ya shika k'warai da aniya daga sannan na sallamawa sha'anin rijalu na sake yin lakwas ina ayyanawa a raina ko ni ce na fadi na mutu mutumin nan damuwarsa k'alilan za ta kasance babu wani abu na jin dad'in rayuwarsa da zai fasa.
Ni gabad'aya ma ban san akan wane alkawari yake magana ba domin tunda suka tafi ba mu samu sukunin yin wasu hirarrakin soyayya ba.
Saukar hannunsa da na ji a kirjina ya sanya ni zabura. Na cire hannun da sauri sai ya had'e yatsunmu wuri d'aya yana bina da wani irin kallo wanda yake ko'karin kassara ni. Nan take tausayin kaina ya rufe ni. Yanzu nan ya gama jadadda irin alhini da kewar tsohuwar matarsa jiya kuma matar da ni da Hauwa muke ganin ya fifitata a kanmu ta fad'i ta mutu yau aka binneta a kabari wai har ya gama alhinin da jimamin yana bijiro da wani shagali da jin dad'in da bai wuce na dan wani lokaci ba.
Cike da kasala ya sake mayar da hannunsa saman kirjina yana tatta'bawa ban yi nawar sake cire hannunsa ba muka kurawa juna ido da kyar na furta." Ba ka ji wani iri ba?
Lumsassun idanuwansa ya bude a dabarbarce ya ce."Na ji sun 'kara girma ko dan na yi kewarsu ne." Raina ya baci da jin amsar da yake ba ni. Wato ma bai fahimci akan abinda nake magana ba sai kawai na yi yun'kurin sauka daga cinyarsa ya kuwa ri'ke ni da kyau irin rikon da baki isa ki k'wace ba.
Sosai na bude idona a kansa na ce." Gaskiya ni ka ba ni mamaki wallahi mutuwa fa aka yi maka mai zafi har alhinin ya bar gangar jikinka kenan."
Ya gyada kansa yana fad'in." To ai ta riga ta rasu Amina, ni na isa na dawo da ita ne? Mutuwar nan kowa zai mutu to me zai sanya a tauyi rayuwa a bawa gangar jiki da ruhi abinda yake muradi kada ki manta ke fa ki ka yi mini alkawari idan na dawo za mu sha soyayya."

Na ce" Da yaushe na yi maka alkawari abinda ma duka bai fi sau biyu muka yi magana ba tunda kuka tafi."
Yana d'an shanshanar jikina kamar wani tsohon zakin da ya jima yana farautar nama ya ce. To ina jin dai a irin mafarke-mafarken da nake yi dake ne ki ka gaya mini za ki yi mini soyayya fitacciya."
Na juya da kaina takaici ya hana ni magana a haka ina jinsa yana ta turmutsa hannunsa cikin rigata. Gabad'aya kaina ya kulle na rasa da wane ma'auni zan auna wannan lamarin

ya gama goge mini duka haddar da na yi a kansa, ai na d'auka na gama karantar halayensa gabad'aya ashe da sauran abinda ban gama sani ba.
Ya d'ora bakinshi saman lebunana ya sumbata kafin ya cire a hankali da wani irin yanayi ya ce." Abin nan yana d'auke hankali Amina zai mantar da ni abubuwa da yawa, bayan kiran sunan Allah a cikin k'unci da damuwa sai wannan lamarin domin ni a wurina ma gaba yake da cin abinci, a wannan dare babu abinda zan fasa ai a haka duniyar ta ginu tun kafin mu zo cikinta ake mutuwa ake muka sunnah irin wadda za mu yi yanzu, mu ji dad'i mu gamsu kuma Ubangijin da ya ce mu yi hakan ya ba mu lada
mai yawa."
Na yi k'asa da kaina dalili ba ni da wani karsashin da zan kalubanci maganarsa ta kowace siga ya fi ni gaskiya amma ai ana barin halas da kunya wallahi har yanzu matar nan idan ta fa'do mini a raina sai gabana ya fadi.
Ya cika ni na sauka kasa yana bude fulas din abinci jikinsa har d'an rawa yake yi ya ce." Abiñci zan baki kici ki koshi kamar yadda ni ma ki ka ciyar da ni daga nan kuma sai mu sake ciyar da juna wani abincin na mussaman ko ba haka ba ne?"
Na ce." Gaskiya ba zan munafurceka ba a yanzu wallahi ba ni da wani karsashin da zan tari wannan lamari daka bijiro da shi. Ka yi hakuri tukkuna dukkunimu hankalinmu ya daidaita sai irin wannan nishadin ya biyo baya."
Ya gyara yanayinsa yana fad'in." Ni ina da karsashina, sannan kuma a cikin nutsuwa da hankalina nake, menene a ciki ne haramun ne, saboda kawai an yi mutuwa sai a ajiye ibadar Allah ba na son jayayya Amina a buk'ace nake ke daga ganin yanayina ma kin san da hakan to me zai sanya ba za ki sama mini da farinciki ba.
Kuka na fara yi tsakani da Allah ni ban san yadda zan yi na tari abinda yake so ba har na taimaka masa ya nisha'dantu irin yadda ya saba, har yanzu jikina babu wani kuzari ni gabad'aya ma duniyar ta fice mini daga raina.

Don dole na dinga kar'bar towon da yake ba ni a bakina ina ci ina goge kwallar da take fitowa daga idona. Da kyar na ci rabin malmala na turje na daina kar'ba muka shiga toilet a tare wai zai yi mini wanka nan ma sai da muka yi kokawa kamar sababbin amare ina share hawayen takaici haka na yi wankan yana tattabe mini jiki muka fito. Towel ne kawai a jikina a daure na d'auki kayana zan sanya ya kwace. Yana fad'in." Sanya kayan ai bashi da amfani Amina, bari tukkuna mu kammala ko?"
Ya ja hannuna zuwa gadonsa zugwi-zugwi haka na bi shi cikin sagewar gwiwa da nadamar rayuwa. Wai shin ma ya za a yi ya nisha'dantu. Tambayar da nake yi wa kaina kenan.
Ya tura ni na yi kwanciyar ringingine dogare kafafuna na yi da zummar tashi ya raba nasa kafafun a kaina ya dabaibayeni. Abubuwa na tashin hankali da gigita lissafi ya fara yi mini jikinsa na wani irin rawa. Na dinga matse jikina ina ya'ki da gangar jikina da zuciyata akan kin 'karbar abinda yake mini, amma ban yi nasara ba, cikin k'ankanin lokaci ya fitar da ni daga hayyacina na kasa gane shin a duniya nake ko ni din ma na shilla barzahu ne ban sani ba. Ki'dima kam da ficewa daga hayyaci mun yi tunda abin ai ba sabo ba ne

a wurinmu ya riga ya gama zame mana jiki sosai ya gurje ni ya gamsu na gamsu babu 'karya. Ashe shima wannan lamarin ba a had'a shi da komai idan gangar jikin ya kar'bi sakon duk turjiyar da zuciya take yi akan hani bata samun nasara. Na dinga jin kunyar kaina da kaina domin kuwa ni kaina da na shiga shu'uni mantawa na yi da cewa rasuwa aka kwatsama mana a gidan sai da tunani da hayyacina ya dawo tukkuna na ji siraran hawaye na gangaro mini ina rayawa a raina idan na riga shi mutuwa haka zai samu wata macen ya cigaba da more rayuwarsa tunda ai gashi ya fad'a. Mata biyu da ya fifita a rayuwarsu har baya iya boye so da k'aunar da yake musu sun mutu yana kewarsu amma bai fasa gudanar da wani lamari ba.

Idan kin karanta ba ki biya ni hakkina ba ina bin ki bashi.

Da asuba na sauka k'asa  bayan fitarsa sallah. Wanka na yi sosai da ruwan d'umi na gasa jikina. Anti Yagana duk tana zaune saman dadduma tana kallona na fito daga bandakin na kintsa jikina sannan na gabatar da sallah. Na shafa a nutse na juyo ina kallonta lokacin ta zame ta kwanta saman dadduma amma ba bacci take yi ba carbin da yake ma'kale a hannunta take ja. A tsanake na gaisheta ba tare da tashi ba ta amsa mini tana kallona kafin ta sauke ajiyar zuciya ta furta." Gobe da wuri zan kama hanya Amina, jiya da daddare Babansu Fadila ya kira yake gaya mini mijinta ya zo ya ga masa bata da lafiya har da su k'arin ruwa."
'Yar dariya na yi kafin na ce." Anti Yagana ta kusa goya jika kenan."
Harara ta mako mini tana tabe bakinta."
Na ce." E, mana anti ai idan ki ka ji an fara da haka to k'aruwa ce."
Ta girgiza kanta tana fad'in. " Yaran yanzu ba sa saurarawa 'ya'yan mutane daka an kai maka yarinya wata d'aya biyu zuwa uku ka had'ata da lalura wasu fa ko shekara ba sa yi suke haihuwa."
Da murmushi a saman fuskarta na ce." Hakane anti Yagana ai gwara matasan su yi auran da wuri ya fi alheri akan su  dinga zinace-zinace kuma bari na gaya miki wani abu ba fa samarin ne kadai suke da wannan 'kawazucin ba har da 'yan matan wallahi dukkaninsu son auran suke yi."
Ta yi shiru tana ta'be bakinta. Na ce." Kawai ki yi mata addu'ar Allah ya raba su lafiya, domin tunda ki ka ji an fara da haka to an gamu."
Ta ce." To Allah Ya raba su lafiya." Na amsa da "Amin ko ke fa."
Muka dan yi shiru na dan wani lokaci kafin ta ce." Wallahi ina tausayawa jama'ar da suke k'arkashin matar nan, da yawa akwai wad'anda suke d'aukar dawainiya mai yawa ta iyali iyaye da yan'uwa duka a 'karkashinta yau gashi ta fad'i ta mutu dole za su shiga wani yanayi wanda ba zai yi musu dadi ba. Su kadai nake tausayawa sosai dalili yaranku da suke ri'ke a hannunta ai jajensu k'alilan ne tunda kuna raye sai ku cigaba da kula da yaranku Amma jama'ar da suke ci da sha a 'kasanta Allah ne kad'ai ya san su."
"Hakane anti Yagana to ya za a yi ne? Lokacin ta ya yi cikinmu gabad'aya babu wanda ya isa ya dakatar da komawarta ga wanda ya halliceta hakika ya fi mu sonta shiyasa ya kira ta zuwa gare shi."

Ta girgiza kanta tana fad'in." Ubangiji Allah Ya sa mu dace amma mutuwa kadai wa'azi idan har za mu hankalta."
Haka muka kasance a d'akin muna  tattauna batutuwa da yawa har garin ya yi haske sosai

Gidan Hajiya Maryam marigayiya.
Yabi ta dube shi yana tsaye a jikin bango ya rungume hannuwansa a k'irji. Bashir ne k'aninsu namiji da ya rage musu a maza tunda d'ayan ya rasu sai shi kad'an yanzu yana can yawon barkinsa ya ji rasuwar. Dukkaninsu sun fi shekara
Takawas rabon da su gan shi, amma dai suna jin labarinsa cewa yana can Legos agege yana harkar sayar da tabar wiwi da sauran kayan gusar da tunani.
Jiya cikin dare ya sauka yau da safe suka wayi gari da tashin hankali domin ya ritsa su a d'aki gabad'aya har da yaran marigayiyar wai sai an raba gado an ba shi rabonsa ya koma bakin sana'arsa. Kana jin irin zantukan da yake yi za ka gane mugun d'an kwaya ne ga wani shegen aski a kansa wandon dake jikinsa duk ya zazzago da iyayen sark'oki rakwacam a wuyansa da tafka-tafkan zobuna a tsayun hannunsa. Su kansu don dai jininsu ne amma bai yi kama da musulunci ba.
Anti Yabi ita ce take bin Maryam shiyasa girman ya koma hannunta gabad'aya yanzu ta dube shi tana fad'in.  Malam yaushe aka yi mutuwar da zaka zo ka daga mana hankali, yaushe rabonmu da kai shekara kusan takwas fa babu wanda kake nema kana can kana yawon iskancinka, ko an gaya maka kowa ma mahaukaci ne irin ka."
Rukky wadda take sakuwarsa ta ce." Anti Yabi rabu dan kutumar......Ba ta kàrasa ba kuwa ya kai mata duka a bakinta yana fad'in." Ni ne dai Bashir ban canza ba zan iya kashe ki anan dan babanki."
Anti Saliha ta ce." Ka kasheta Bashir."
Da sauri ya furta." E, dan babanta ta k'ara sa mini baki ina magana sai na cire mata ma'kogwaro wallahi."
Nabila ta ce." Kai ka shiga hankalinka fa wallahi idan har ka ce za ka daga mana hankali zan sanya a rufe mini kai, haba ina dalili kuma ke anti Yabi da kuke maganar gado uban wanene ya ce muna da gadonta tana fa da miji da yara maza biyu a ciki a iya sanina ba mu da abinda za mu samu a dukiyar anti Maryam."
Rukky ta ce." Ai dama dole ki fad'i haka mana tunda ke kin san kina tare da ita duk wasu muhimmai abubuwanta suna hannunki kin fi kowa sanin sirrinta da dukiyarta dole ne ki fad'i haka."
Yabi ta ce." Wannan zancen banza kike yi Nabila kada ma ki kuskura ki zo da wannan maganar domin kuwa kin fi kowa sanin sirrin Maryam ko mun gaje ta ko ba mu gaje ta ba ba zamu tashi daga zaman makokin nan a banza ba.
Nusaiba ta fashe da kuka! da sauri duka suka juya suna kallonta don wata'kila sun manta da cewa yaran suna wurin. Ta tashi da sauri ta fita tana goge hawaye Salim da Adam suka bi bayanta cikin damuwa mai yawan gaske.

Suna fitowa suka ganta a tsaye a tsakiyar falo tana kuka tuk'uru. Salim ya ja hannunta da sauri suka nufi d'akinsu domin da akwai sauran bak'in da suka kwana a gidan dangin Babansu kakarsu ma Hajiya Ayya tana nan da wasu daga cikin 'yan uwanta.
Tana kuka ta ce." Allah Ya sa duka katikan Momi na banki suna hannuna. Mukullin dirowar nan ne ban san inda yake ba. Amma tun ranar da za su koma asibiti na kwashe katikan bakinta."
Salim ya ce." Yanzu ya za mu yi anti Nusaiba mu gayawa Hajiya Ayya ko Baba Tajo."
Adam da tunda suka fara maganar bai ce komai sai yanzu ya ce." A a ba yanzu ba tukkuna tunda ko sadakar uku da ba a yi ba, mu bari mutane su watse sai mu sanar da Baba. Anti Nusaiba duk rintsi kada ki gaya musu cewa." Katin bankunan da take ajiya suna hannunki."
Ta gyad'a kanta tare sanya hannu tana goge hawayen da ta kasa tsayar dashi cikin damuwa ta furta." Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wayyo Allah Momi!"
Adam ya je ya rungumeta sosai suka zauna gefan gado yana rarrashinta Salim din shima ya zauna gefenta jikinsa a mutukar sanyaye......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi

na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book 2k complete on telegram what'sapp Gruop Kuma 1k via 0542382124.... Binta Umar gtbank.*
*07084653262*
*120*
Yusi Ya fito daga toilet ya same su a zaune shiru. Ganin Nusaiba a d'akin ya sanya shi d'an sakin fuska ya gaisheta cikin girmamawa ta amsa da yanayi na damuwar da take ciki ta tashi ta fita. Adam ya mike babu kuzari ya shiga toilet din domin yin wanka. Shi kuma Salim ya tashi ya fita daga d'akin. Daga lokacin ya fahimci cewa bayan damuwar da suke ciki ta rashin mahaifiyarsu akwai wadda ta k'aru duk da bai ji komai ba ya san abinda suke tattaunawa a kai ba mai dad'i ba ne.
Yana nan zaune cikin zullumi da nazarin yadda rayuwar 'ya'ya take sauyawa idan suka rasa wani jigo Adam din ya fito a gurguje ya shirya suka fito falon tare wanda ya yi daidai da lokacin da Mairo ta fito tare kaf da yaran kowanne cikin tsafta. Suka nufi masaukin Hajiya Ayya mahaifiyar Alhaji Amadu kenan wadda take tare da jama'arta. Bayan sun gaisa anan wajenta yaran suka zauna twins da Minal tunda Mairo tana can suna hidimar d'orawa da saukewa kamar yadda al'ada ta zama a gidan mutuwa.
Yusi ya ri'ke hannun Khalil suka fita tare domin duk zaman da ake yi na makoki da yaron suke zaune gabad'aya gaban babansu suna kar'bar gaisuwar tare.
Shi ma bai jima da zama a wurin ba suka fito can suka hange shi yana kar'bar gaisuwa daga jama'ar da suka yi dafifi domin jiran fitowarsa.
Muna zaune a falo gabad'aya har da su Hajja duk sun yi wanka sun fito ina ta kallon yadda inna Uwani take nan nan da Hajja har goya Sultan a bayanta tana ta jijjigashi duk da ba kuka yake yi ba. Sai ta ba ni tausayi sosai domin duk tana yin hakan ne domin dakushe lefin 'yarta amma ai ba haushe yace tun ran gini ran zane Hauwa ta bata goma daya bata gyaru ba, duk da gaskiyarta babu wanda zai gani saboda abinda tayi a yanzu ya dusashe lefin da take ji an yi mata.

Suka shigo a tare su uku har da Khali da ya d'an fara tasawa abinda yake burgeni da yaron nutsuwa sam bashi da hayaniya ba za ka ta'ba cewa Tajo da Hauwa ne suka haife shi ba.
Har suka 'karaso wurin da muke zaune ban d'auke idona daga kansu ba, wannan abota da soyayyar ta Yusi da Adamu sai Allah had'uwar jini babu dangantaka ko kad'an sai ta addinin islama.
Duka muka gaisa a tsanake don d'aya bayan daya suka bi suka gaisa da kowa. Na kasa janye idona daga kan Yusi ganin yadda ya kara zama saurayi wannan jikin da ake yi masa tsiya a kai duk ya rairaye da akwai dai amma ba kamar lokacin da yake tashar kuruciya ba.
Ganin kallon da nake yi masa ya yi yawa ya sanya ya sunkuyar da kansa yana d'an kalato murmushi ya sake fad'in ." Mama ya karin hakuri."
A tak'aice na ce." Ai ku zan yi wa ta'aziyya ko Adamu."
Ya d'an saki fuska kad'an amma bai ce komai ba sai tausayinsa ya sake kama ni.
Na ce." Allah Ya yi mata rahama Annabi ya san da zuwanta. " Gabad'aya muka amsa da Amin har ni da na yi. Addu'ar. Sun d'an jima a tare damu kafin su fita Adam yana tambayar Kamalu na ce ai shi tun sassafe ya fita don ya riga ma maigidan zama a wajen.
Gabansa suka je suka zauna gabad'aya har Salim ya dube shi yana fad'in." Ku kunna wayarta ku sanar da rasuwar duk da nasan da yawa wasu daga cikin abokan nan kasuwancinta sun san ta rasu tunda an yi jana'iza da wasu amma dai
a tambayi idan da wanda yake bin ta bashi ya fad'a a sauke mata nauyi daga nan zuwa ranar da za a yi addu'ar bakwai. Sannan ka nemi yaranta ina nufin wad'anda suke yi mata hidima ta kasuwanci idan da wanda yake da hakki a kanta ya fad'i a biya shi. Sanin da na yi ita mai bayarwa ce amma hakan ba zai hana a bibiyi abubuwan da ta wanzar a lokacin da take rayuwa ba, wannan shine gatan da ni daku zamu yi mata bayan addu'a."
Ya amsa cikin ladabi tare da tashi da sauri can rumfar da ya hangi yaranta sun zauna jiya ya nufa wasu sun zo daga ciki wasu kuma ba su zo ba kawai sai ya nufi cikin gidan domin kar'bo wayarta dake hannun Nusaiba tunda Allah Ya taimaka har da manyan wayoyinta masu tsada ta kwashe a lokacin da ta had'a da katin cire kudinta.

Yana nan zaune jama'a na 'barkowa ta ko'ina abokanansa wasu daga cikin abokanan tsohon mijinta da 'yan uwansa dama wasu sam da bai san daga ina suke ba sukan tsuguna  gabansa da tafka tafka rawaninsu a kan su suna yi masa gaisuwa.
Wani daga cikin masu rawanin ya sake komawa wajansa ya gurfana Yana fad'in." Allah Ya taimake yanzu yaron mai rasuwar na ji yana magana a wajan da muke zaune cewa idan da wanda yake bin marigiyar bashi ya fad'a, to ina daya daga cikin wad'anda ta sanya a aiki."
Ya dube shi a tsanake kafin ya furta.''  Wane aiki ka yi mata, kuma nawa ne hakkin naka?"

Ya gyad'a kansa tare da dan juyawa yana waiwaye akwai jama'a sosai don dai hayaniya tayi yawa amma duk da hakan ko da suke maganar bai fasa kar'bar gaisuwa ba tunda har yanzu shigowa ake yi.
Cikin nazari ya ce." Ko akwai buk'atar sirri ne?"
Da sauri ya d'aga kansa yana fad'in."E, kwarai kuwa Yallabai."
Sai ya ce." To babu damuwa fita waje  ka tsaya jikin gate zan fito yanzu na same ka."
Ya kuwa tashi da sauri yana sa'be babbar riga ya kama hanyar fita. Ya bi shi da kallon nazari kamar akwai rashin gaskiya a tare da shi. Yaran duk suna gefensa a zaune ya tashi ya bi bayansa.
Ya zuba hannuwansa duka biyun cikin aljihun tazarcen dake jikinsa tare da fad'in." To ina jin ka Allah Ya gafarta Malam."
Ya risinar da kansa yana fad'in." Hakika Maryam ta sanya ni aiki babba a wannan tsukin da Ubangiji Allah Ya d'auki rayuwata. Mun gama magana da ita akan kudin kayan aiki da duk abinda za a buk'ata wurin biyan buk'ata dubu dari bakwai da ashirin to sai ta kwanta ciwon nan da bata tashi ba daga shi kuma ba ta turo mini kudin ba ni kuma na juya dana hannuna na fara aiki domin nasan bata da wasa akan samun biyan bukatarta wallahi yanzu haka daf nake da kammala aikin kwatsam sai rasuwarta na ji kuma dama a satikan da suka wuce ba ni samun wayarta hankali ya tashi wallahi domin na riga na juya mata kuma kaf abinda yake hannuna kenan."
A tsanake ya ce." Wane aiki ne? kuma nawa ne kudinka."
Ya yi dan Jim kafin ya ce ." Duka dubu dari bakwai ne da ashirin kamar yadda na gaya maka da farko abinda ya ja kud'i shine rago mai tozali da muka nema akan aikin. Sai fatar karsana sannan mun nemo zuciyar jemage, akwai kuma kaji da muka saya jan zakara, wake-wake ba'kar kaza da kuma turarukan da muka saya wurin yin aikin."
Shiru ya ratsa wajan bayan gama maganarsa. Ya ce." To, na ji wane aiki aka yi akan hakan."
Ya yi shiru tare da yin kasa da kansa sai da ya kara maimaita tambayarsa tukkuna ya ce." Alhaji a zahirin gaskiya ni ina daya daga cikin manyan Malam Hajiya Maryam kuma duk lokacin da ta buk'aci wani aiki muna ko'karin ganin mun gudanar dashi duk rintsi domin samun biyan buk'ata. Wannan sirri ne tsakani na da ita amma yanzu ta ta 'kare sai dai mu ro'ka mata gafara wurin Ubangiji. Dole ta sanya ni neman ha'kkina domin dai aiki gaf nake da kammala shi rasuwarta ta katse na taho. Kuma kudin hannuna sun yanke Hajiya Maryam aiki ta sanya ni na yi akan wata baiwar Allah mai suna Hauwa. Yadda take gaya mini cewa tunda take a duniya ba a ta'ba yi mata tozarcin da matar ta yi mata ba shine dalilin da ya sanya take so a d'ora mata jinyya mai tsanani ko kuma a shafe ji da ganinta ta yi mutuwar tsaye babu ji babu gani cikin biyu tace ayi daya. Duk abinda na lissafo maka da farko na saya na kuma fara aikin sai dai ban kammala ba, Allah ya yi mata rasuwa.
K'warai da gaske ya tsorata tun lokacin da mutumin ya fara magana. Mazantaka kawai ya nuna tare da gogewa ta fannin mu'amula bai nuna masa razani ba.

Ya ce." Yanzu ya ake ciki idan ka koma za ka kammala aikin ko kuwa?"
Sai ya gyad'a kansa yana fad'in." Zan dakata gaskiya tunda Allah ya yi ikonsa akan wadda ta sanya ni sai dai da iska (jinnu) muke yi su kuma ba alkawari ne da su ba, idan na gaya musu mu tsaya da yin aikin bai zama lallai su tsaya kai tsaye sai sun gindaya abinda suke buk'ata amma ba zai wuce yanka ba."
Ya girgiza kansa cikin d'an karan mamaki da al'ajabi cikin zuciyarsa tana nanata istigifari. Ya dube shi kafin ya ce." Ka kyauta da ka d'auki aniyyar dakatawa zan kuma biya ka hakkinka. Amma ba yau ba ina so ka dawo bayan sadakar bakwai kud'i hannu da hannu."
Ya risinar da kansa yana ta godiya. Shi kuma ya yi ta nazarinsa cike da madaukakin mamaki gashi cikakken mutum cikin manyan kaya da kamala har da rawani ashe mushiriki ne ta'babbe ne, wato iskokan da suke yi musu aiki sune masu biyan buk'ata ba Allah ba.
Ya sanya hannu cikin aljihu dubu ashirin ya bashi kafin ya ce ." Ka yi kudin motar komawa gida amma kamar yadda na gaya maka bayan an yi addu'ar bakwai ka zo ka kar'bi kudinka."
Ya kar'ba da sauri yasa a aljihu yana ta godiya ya mika masa hannu wai su yi sallama bai kar'ba ba kawai sai ya daga masa hannu yana fad'in "A sauka lafiya." Daga haka ya koma cikin gidan cike da tunani da nazari..
Ya samu Bashir tare da su Salim da Yusi a zaune. Kallo guda ya yi wa yaron ya hangi kama sosai da Maryam domin duk irin fuskarsu daya sai dai shi fuskarsa ta yi duhu sosai da lebensa tabbacin wiwi ta ratsa shi.
Ya dinga sunkuyar da kansa kasa kamar munafiki ya fara gaishe shi cikin ladabi irin wanda suka saba.
Ya amsa yana dubansa tare da fad'in." Ko kaine Bashir din ne?''
Da sauri ya ce." Ni ne, eh ni ne?''
Ya fad'a yana wata dariya da sosa kansa.
Shigowar Alhaji Sulaiman gidan da iyalinsa ya d'auke masa hankali, da kansa ya tafi domin tar'barsa tun kafin ya karaso rumfar da suke zaune.

Tare muka yini da Hajiya azizi da abokiyar zamanta mai suna Hajiya Salamatu da Halisa 'kanwarta da ta ba ni labarinta kwanakin baya. Muka yini dasu a gidan sai wajan uku na rana bayan sun ci abinci sun yi salla muka yi sallama da su kan cewa za su shiga can gidan Maryam din domin yi wa danginta ta'aziyya na yi ta mamaki ashe ba su shiga ba sai yanzu da suka tashi tafiya.
Alhaji Sulaiman ya shigo har gida ya yi mana gaisuwa ni da Hajja ya d'an jima a tare da Hajja suna hira kafin ya yi mana sallama ya fita.
Daf da magriba mun d'an samu sau'ki shige da fice na mutane domin duk wanda ya je can gidanta ya yi gaisuwa sai ya shigo mini mussaman mak'otanmu dama wad'anda muke cikin estate din a tare.
Na shiga d'aki sallah na samu Anti Yagana har ta idar ta kashingida tana fad'in." Gobe ana yin addu'a da safe zan d'auki hanya da wuri Amina."
Na ce" Ba za ki ta ya ni zama ba anti Yagana kina ji su Hajja ma fa gobe suke cewa za su tafi."

Ta furta." Na so hakan Amina Amma hankalina ya yi gida saboda Fadila ban san a wane yanayi take ciki ba tunda an ce har da karin ruwa."
Na ce." Hakane kuma to shikkenan Allah ya kaimu zan gayawa maigidan idan ya shigo in sha Allahu."
Ba tace komai ba. Na shige band'akin domin d'aura alwalar sallar magriba.

Har bayan isha'i muna tare da anti Yagana a d'aki muna tattauna mas'aloli masu yawa. Hajja ta shigo d'akin da kanta tana fad'in." Yagana tun safe da ki ka fito mu ka gaisa ki ka auri zaman d'aki ko ba kya jin dadi ne."
Ta mike zaune tana yar dariya kafin tace." Wallahi lafiyata lau Hajja kawai gajiyar tafiya ce bata sake ni ba."
Itama da murmushi da kulawa ta ce." To ku fito mu ci abinci, ke Amina kema tun d'azu nake hankalce dake kowa ya ci abincin rana babu ke, maza ku fito mu had'u mu ci abinci yanzu nan Tabawa ta kammala har ta fito mana dashi."
Na ce." To shikkenan Hajja.''
Anti Yagana ta yi murmushi bayan fitarta daga d'akin tana fad'in."Baiwar Allah nan tana sona Amina, ko da yake k'aunar da take yi miki ne ta shafe ni."
Na ce." K'warai kuwa na sheda soyayyata da Hajja ta daban ce, amma shekarun baya anti Yagana an so a juyar mata da hankali wallahi na d'an fuskanci gizago daga wurinta da na ri'ke addu'a kuma sai abin ya shud'e kamar ba a yi ba."
Ta ce." Muddin baka nufi kowa da sharri ba Amina to ko shi ya nufe ka dashi ba zai yi tasiri ba, addu'ar nan dai da ki ka rike ki ajiye a ranki cewa itace makaminki."
Na ce." In sha Allahu anti Yagana."
Tare muka fito falon duk suna zaune wannan karon Sultan yana hannun gwaggo tana d'an jijjigashi.
Kafin na zauna na ce." Gwaggo yau kece ki ke auran kenan." Tana dariya take fad'in.'' E, ai yau yace da ni yake auran."
Ina Uwani ta yi murmushi tana cewa." An jima kadan zai ce da tsohuwar zuma ake magani ni ce uwargidansa. Hajja da tunda suke maganar ba ta sanya musu baki ba sai yanzu ta ce." Duk ku gama yin jigila dashi yace ni yake so ko Tabawa." Aka yi dariya gabad'aya cikin raha da barkwanci.
Cikin wannan yanayin ya shigo tare da Kamalu dama a tare nake ganinsu duk lokacin da suka tashi daga kar'bar ta'aziyyar.
Ya tsaya suka gaisa da su Hajja kafin ya haye sama. Shi kuma Kamalu ya zauna a cikinmu Hajja ta ce Baba Tabawa ta zuba masa abinci.
Saman na bi shi ina shiga d'akin na same shi ringine a gado. Na k'àrasa na zauna gefan kafafunsa. Ya tashi zaune yana sauke ajiyar zuciya." Na gaji tubis Amina ga'bobina ciwo suke yi mini wallahi na jima ban yi gajiya irin ta wannan lokacin ba."
Na sauke ajiyar zuciya Ina fad'in." Ya za a yi abu ne da aka asassa shi amma da yawa wasu ba sa yin wannan zaman."

Ya ce." K'warai kuwa gobe idan an yi addu'ar uku zan sanya a cire rumfunan da aka kafa kowa ya tafi kuma haka ya isa ranar bakwai zan sanya masallatai a yi mata addu'a."
Shiru na yi ban ce komai ba.
Gabad'aya tunanina na kan yaranmu. Amma har yanzu ban ji yace komai ba akansu. Ba ni son na yi magana ta zama fitina zan d'an jira shi daga nan zuwa ranar da za ta cika kwanaki bakwai duk wacce za mu yi sai mu yi.
Ya yun'kura zai tashi sai ya koma ya zauna. Na ri'ko hannunsa cikin mamaki ina kallonsa lallai da gaske ya gaji. Hannunsa da na ri'ke na ji d'umi ba kamar koyaushe ba. Sai kawai na ta'ba wuyansa zafi rad'au zazza'bi ne.
Na ce." Zazza'bi kake yi fa Baba?"
Ya ce." Zazza'bi ne ko?''
Wai tambaya yake yi. Na ce." K'warai kuwa zazza'bi ne ya kawo maka sagewar gabobi da ciwon jiki, ya kamata ka samu hutu fa."
Ya sake yun'kurawa a karo na biyu yana fad'in." Bari na yi wanka zan kira likitana yanzu ya duba ni tun wajan sha biyu na rana na ji yanayin jikina ya canza ina dan jin ciwon kai ma."
Na kama hannunsa muka nufi bandakin tare na hada masa ruwan wankan ina fad'in.'" Wankan ma da ka bar shi tunda ka yi da safe. " Ya ce." Ai ba zan iya bacci ba idan ban yi shi ba Amina, kada ki damu bari na yi na fito ki kawo mini abinci."
Na ce." To a sanyaye na fito na bar shi a toilet din na sau'ka kasa cikin 'yar damuwa ya jima kuwa bai kwanta ciwo ba tun bayan zazzafar murar da ya yi a gidana sakamakon ruwan saman da ya dake shi a shekarun baya.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *Gudun aure paid book. 2k complete on telegram. What'sappa Gruop 1k Via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*121*
Lokacin da na koma d'akin bai fito ba na zauna ina jiransa ya fito a rikice da d'ari irin na zazzabin ya sake ninkuwa kaya masu d'an kauri na d'auko masa ya kar'ba yana ko'karin sanyawa ya ce na d'auko masa hular sanyi duk a cikin kayan nasa ina fad'in." Abinda nake ta gudu kenan. Ya gama sanya kayan jikinsa ya zauna gefan gado cikin yanayi na ciwo da kaina na shafa masa basiline a jikinsa gabad'aya. Ya sanya hular har ta rufe kunnuwansa. Kafin na fara zuba masa abincin ya d'auki wayarsa ina jin ya kira likitansa ya yi masa bayani ya bashi tabbacin cewa gashi nan zuwa yanzu.
Cokali biyu ya iya ci na abincin ya dakata. Gabad'aya ni ma sai na ji zazzabin yana nema ya rufe ni. Babu zato ba tare da tsammani ba na ji yana fad'in." Kira mini Hauwa a wayarki Amina."
Da mamaki mai yawa nake dubansa. Ya d'an lumshe idonsa kafin ya bud'e yana gyad'a mini kai.
Ban iya cewa komai ba na tashi a hankali na sauka kasa da nazari a k'wanyata. To ko dai an daidaitasu ne ban sani ba wata'kila kafin mu fito daga d'aki ni da Sahura mahaifiyarsa ta zauna dashi akan hakan zuciyata ta

dinga yi mini sa'ke-sa'ke. Na koma d'akin na same shi a takure a gado ga blanket din bai rufa ba.
Na zauna tare da rufe masa k'afafunsa har zuwa saman kirjinsa sannan a tsanake na fara neman layin Hauwa. Bugun farko ta daga ta kama sunana. Na amsa kafin mu gaisa ban ji ta sake yin gaisuwa ba kawai ta yi shiru sai na daure na ce." Maigidan ne yake son magana dake?"
A yatsine tace." Kamar yaya menene a tsakanina da shi, kuma ai yana da lambata mai ya sanya sai kece za ki kira ni.''
Na danne b'acin ran da nake ji yana taso mini na furta." Haka dai ya ce ni na kira ki Hauwa."
Ta ja siririn tsaki wanda ya yi mini ciwo sosai a rai amma ban katse wayar ba na mik'a masa yana daga kwance don bai tashi ba ya kar'bi wayar yasa a kunnansa. Sunanta ya kira ta amsa a dakile.
Ya d'an yi jim ban sani ba ko yana jiran gaisuwarta ne ko kuma yana jiran ta yi masa ta'aziyya ko daya dai ba ta yi ba.
Ya furta." Kina lafiya ko?''
"Umm" Ta ce cikin basarwa. Ya yi shiru na d'an wani lokaci kafin ya furta." Idan kin ji wani canji ko yaya ne a jikinki kada ki yi shiru."
Na yi zugum ina kallonsa da mamaki wai yau Hauwa yake rarrashi har yana fad'in idan ta ji canji na ciwo a jikinta kada ta yi shiru ta sanar da shi. Duk ina k'iyayyar da yake fadin yana yi mata. Mamaki ya kasa bari na janye idona daga kansa har sai da suka yi sallama ya miko mini tare da lumshe idonsa. Na daure ina fad'in." Alhamdulillahi na ji dadin wannan abin da ya faru, Ina fatan Allah Ya sa ya zama na karshe."
Ya yi shiru bai ce mini komai ba. Ni ma na yi shiru ina d'an duba wayata sai dai can kasan zuciyata wani takaici ne na dinga tunanin daga ina yake ai ni nake so Hauwa ta dawo mu cigaba da zama to mai zai sanya don ya yi waya daya da ita yau na ji haushi idan hakane kuwa gaskiya zuciyata bata kyauta mini ba.
Ban iya tashi na fita daga d'akin ba har sai da likitansa ya zo ya duba shi sosai ya yi masa BF domin yana kuka da ciwon kai sosai jininsa ya haura amma ba sosai ba, dama kuma yana da hawan jinin sai dai ba kasafai yake tashi ba sai da damuwa kamar shakarun baya da ya motsa masa lokacin ina amarya yana neman hanyar da zai samu kaina ni kuma na'ki bada fuskar hakan  tun zamana na farko Legos kenan a iya sanina tun daga lokacin bai kara motsa masa ba sai yanzu.
Suka yi sallama yana fad'in " Za su tafi da Sukairaju yanzun domin ya bashi magunguña. Ya ce mini lallai ya ci abinci sosai kafin ace ya sha maganin.
Da kyar da jibin goshi kamar wani yaro ko d'an yayen da yake rigima ya ci cokali biyar bayan biyun da ya ci da farko yana fad'in bakinsa babu dad'i, ba zai iya ci da yawa ba. Haka nan na ha'kura na kyale shi tunda iya naci da magiya na yi masa akan ya kara yace a a.
Sukairaju ya kawo magunguñan ya tsaya ya yi masa sannu kafin ya fita. Na duba kowanne akwai yadda za a ba shi.
Na dube shi idonsa biyu rufe idon kawai Yayi kamar mai bacci.
Na ce." Ka tashi kasha maganin to."

Bai yi mini jayayya ba ya tashi na d'auki ruwa na tsiyaya a cup na mik'a masa ina ciro maganin ina bashi yana sha tsaf ya gama ya ajiye zai kwanta na ce." Ka dan bari ya fad'a maka." Bai ji ba ya yi kwanciyarsa minti biyu kuwa sai yun'kurin amai. Ya tashi da azama ya nufi toilet ya fara watso shi duk abincin da yaci da maganin da sha suka yo waje.
Na rasa yadda zan yi gabad'aya damuwa ta dabaibayi ni. Haka nan na tarairayo shi muka fito ya je ya kwanta ya nishi. Na lura baya son ciwo kuma bashi da wani dauriya idan bashi da lafiya haka ya yi mini lokacin da ya kwanta ciwon mura a gidana na kuntau na sha dawaniya.
Toilet na gyara na fito na same shi bacci ya d'auke shi sosai. Aikuwa ba zai yiwu ba, tashinsa na shiga yi ya bude idonsa na ce." Dole fa sai ka tashi ka sake cin wani abincin da maganin idan yaso sai ka yi baccin."
Bai ce komai ba ya gyara kwanciyarsa ya rufe Ido.
Na ce." Ka tashi don Allah ka ji.''
Ya yi mini shiru bai motsa ba. Kawai sai na zuba masa ido tsabar takaici da damuwa na ce." Shikkenan gaskiya zan sanar da Hajja an ta'ba yin ciwo ba cin abinci da magani."
Ya bude idon yana kallona yace." Wai ba na ci ba ne?".
Na ce." To nawa yake wanda ka ci, kuma duk ka amayar dashi da maganin."
Ya tashi zaune tare da tallafe ha'barsa. Sosai na zura masa ido ina nazarinsa sai nake ganin kamar bayan ciwon da yake damunsa akwai wata damuwar. Zuciyata ta fara raya mini ko ya fara kewar matarsa ne da ta rasu. Wani sashe na daban yake ce mini 'Anya kuwa' ai an yi masa mace-mace da yawa ya ha'kura kuma bai ta'ba yin wani ciwo ba, kawai dai ciwon ne ya zo masa akan ga'ba ne.
Nasa hannu na cire hannunsa da ya tallefe ha'barsa da shi a d'an sanyaye na ce." Wai menene don Allah,  kada ka jefe ni cikin tashin hankali, yau kana tallafe ha'ba ko akwai wani abu da yake damunka?"
Ya dube ni. Muka tsirawa juna ido sosai mun jima a haka bai ce komai ba sai ni na janye idona na sake zubo masa abincin da kaina na dinga bashi cikin ikon Allah kuwa ya ci da yawa da kamar minti goma tukkuna na sake bashi maganin a karo na biyu, ban yarda ya kwanta ba sai da muka yi zaman kimanin minti ashirin har ya fara gyangyadi sannan ya kwanta ni kuma na sauka k'asa.
Na samu anti Yagana ta jima da yin bacci. wanka na yi a gurguje na sanya kayan bacci tare da a turare a jikina na koma saman. Lokacin baccinsa ya yi nisa sosai, na shiga cikin bargon kusa dashi sosai na kwanta kafin na fara yin addu'ar kwanciya bacci.
Da asuba da d'an kuzari ya tashi domin ya riga ni ma tashi motsinsa na ji a bandaki na yun'kura da sauri na dira daga gadon domin ina tsoron ya ce zai watsawa jikinsa ruwa. Na same shi yana alwala sai na sauke ajiyar zuciya na tsaya har ya kammala tukkuna ya fita zuwa massalaci sannan shiga toilet din sosai domin yin nawa uzurin.

Tun bayan da ya fita da asuban bai dawo ba sai wajejan goma da arba'in na safe. Na d'an shiga yar damuwa saboda yanayin jikinsa. Amma nasan abinda

ya zaunar dashi bai wuce yin addu'a  ba kamar yadda aka yi duk ranar da mamaci ya cika kwanaki uku da rasuwa.
Anti Yagana Hajja da inna Uwani Gwaggo sun shirya tsaf da Shirin tafiya muna falo da su gabad'aya domin jiran shigowarsa Kamalu ya riga shi shigowa da kusan minti goma kafin ya shigo.

idan kin karanta ba ki biya ni ba ina bin ki bashi.

Cikinmu ya zo ya zauna kujera kusa da ni. Suka gaisa sosai. Hajja ta gaya masa tafiya za su yi. Na d'auka zai  ce su yi hakuri su bari ayi bakwai sai bai nuna damuwarsa akan hakan ba ya ce ." Ita anti Yagana ta bari zuwa an jima kadan Sukairaju ya dawo sai ya d'auketa a mota ya kaita har gida. Hajja kuwa dama a babbar mota suka zo da direbanta duk zai kwashe su har Hajiya Saratu Kamalu da Yusi da Shima shigowarsa kenan yanzu a lokacin da suke maganar cikin shiri tunda ya san da tafiyar tun jiya 'dan uwansa ya gaya masa
Cike da damuwa muka yi sallama na kasa daurewa sai da na yi kwalla na d'auko hijabi muka bi bayansu harbar gidan ni da anti Yagana har sai da suka shiga mota suka tafi tukkuna muka koma cikin gidan.
Anti Yagana ta koma d'aki ta kwanta jiran dawowar Sukairaju kamar yadda maigidan ya fad'a.
Na bi shi saman na same shi a kwance.
Na zauna a d'an sanyaye ina fad'in." Ina kwana?''
Ya tashi zaune yana amsa da kulawa tare da tsira mini ido. Tun jiya yawan kallon nan da yake yi mini ya fara damuna."
Na ce." Ji ki ya yi sau'ki ko?"
Ya gyad'a kansa yana fadin." Alhamdulillahi, na ji sau'ki ina godiya."
A tak'aice na furta." Me za ka ci yanzu?"
"Shayi kawai zan sha idan da hali a yi mini farfesun kifi bakina babu test ko daya."
Na ce." Da hali mana da kaina ma zan yi maka sai ka had'a da bread ko?"
A tak'aice ya ce." Amma fara had'a mini tea din."
Na tashi na sauka kasa kicin na nufa Baba Tabawa tana ta gyare-gyare tare da wanke kwanunan da aka yi karin kummalo na  hada duk abinda zai buk'ata na kai masa.
Na sake komawa kicin din Baba tana fad'in na bari ta yi na ce mata a a kawai ta bari ta huta jiki da jini tun asuba take tashi tunda aka yi rasuwar nan ga hidima da Sultan dama wani lokacin yana hannun inna uwani ko Gwaggo.
Farfensun ya yi masa dad'i sosai kuma ya sha da yawa ya hada da bread har da gyasa Yana fad'in." Ya yi mini dad'i sosai na gode."
Na ce." Sai shan magani?"
Ya gyad'a kansa yana dan murmushi na dinga cirowa ina bashi daya bayan d'aya ya sha. Sannan ya kwanta yana. yi mini godiya.
Sai wajan sha biyu muka yi sallama da anti Yagana wai ita da ta zo gaisuwa har sai da ya bata kudi bayan sanyawa da ya yi a kaita. Tare muka fito har da

shi muka yi mata rakiya Sukairaju ya d'auketa a mota tana d'ago mana hannu.

Gidan ya kasance shiru kowa ya watse gabad'aya ma area ta yi tsit kamar ba a yi wata hada-hada ta jama'a ba tunda zahirin gaskiya ta samu mutane wannan kuma yana da ala'ka da su waye mazajen da ta aura da kuma fannin kasuwancinta sai danginsu daga can jos din da suka dinga zuwa.

Tun da ya yi sallar azuhur ya kwanta sai daf da la'asar tukkuna na tashe shi. Ya tashi kuwa da kuzari sosai ya ce zai yi wanka na ce a a tunda la'asar ce babu kyau haka annabi ya ce. Kuma gashi ba shi da lafiya.
Yana d'an murmushi ya ce." Ban ta'ba jin wannan hadisin ba Amina, sannan a ina aka ce idan mutum ba shi da lafiya ya daina wanka, ba zan iya ba gaskiya."
Na b'ata rai ina fad'in." Wallahi haka aka ce babu kyàu wankan daf da la'asar da bacci. Sannan kuma duk mai zazza'bi bayan son ruwa sai ka ga ciwon ya sake tsananta ka manta jiya kana zubawa jikinka ruwa ya rikice."
Ya ce." Kwarai kuwa hakane amma ai yau gabad'aya ban yi wankan ba fa tun safe kin ga kuwa babu lefi don na yi yanzu, tunda na ji sau'ki gaskiya."
Na ce." Kadai bari sai da daddare idan za ka kwanta."
Bai ce komai ba ya nufi  toilet din ba bi shi a baya sai naga yana burush ina tsaye ina kallonsa ya gama ya daura alwala ya fito.

To a daran ranar can gidan Hajiya Maryam dai ba su rintsa ba duk da an cire rumfuna kuma maigidan ya sallami kowa amma su anti Yabi ba su tafi ba. Ita Nabila dama ta ci alwashin zama domin ta cigaba da kula da yaran. Anti Yabi Saliha da Rukky da shi Bashir din suka zauna wai sai an yi bakwai sai gidan ya kasance sai su kadai da masu aiki Taburni da Mairo sai yara Khalil Twins da Minal da suke hannun Mairo domin itace jigon kula da su shi Khalil yana tare da Adam tare suke kwana dakinsu daya itama Nusaiba tana nan ba ta tafi ba tukkuna.
Talatainin dare wajan biyu da yan mintina duk sun yi bacci Bashir ya kusa kansa d'akin da suke kwance wanda ya kasance nan ne bedroom din Maryam din matattarar sirrinta anan suke ta dabdalarsu. Anti Yabi da  Saliha sun yi washar da su a makad'ed'an gadonta suna ta bacci yayin da Nabila ke kwance kasan kafet ita kuma Rukky na can kan wata shirgegiyar kujera dake can gefa bacci ya shammceta ta bar wayarta a kunne tana yi kallo take yi wata'kila baccin ya cimmata.
A kan Nabila ya tsaya yana fad'in." Ta shi, ke anti Nabila."
Ta tashi zumbur ta ganshi a tsaye dogare a kanta ta ce." Baka da hankali za ka shigo mana a wannan daran wai Bashir me yake damunka ne?"
Ya ce." Na gaya miki tun muna sheda juna ku sallame ni na ware, idan ba haka ba wallahi sai na yi muku illah."
Ta mutsika idonta sosai tana fad'in.'' Dame zan sallama ka Bashir na rantse da girman Allah zan yi magan..... Ba ta kàrasa ba ya fille 'yar k'aramar askar da take hannunsa mai bala'in kaifi ya yi mata bille a kumatu gefan idonta.

Cikin tsananin kid'ima da tashin hankali ta kurma ihu! jini ya mamayeta fuska tunda askar ta shiga sosai kuma ta samu tsokar kumatu.
Gabad'aya suka tashi zaune.
Ya dinga bin su daya bayan d'aya yana fad'in." Illa zan yi muku na rantse da girman Allah idan ba ku fito da abinda yake rabo na ba kun ba ni, shegu yan iska taron tsintsiya babu shara, wallahi zan tsinke miki yatsun hannunki anti Yabi."
Ya dumfareta a zabure yana rangaji da askar a hannunsa mai la'kanin gayawa jini na wuce.... Suka yi tsuru-tsuru ganin yadda fuskar Nabila ta yi gaja-gaja da jini tana ta kuka.
Anti Yabi ta nuna masa kusa da ita tana fad'in." Zo ka zauna nan kusa da ni Bashir mu yi magana ka ji ko, kada ka sake illata kowa a cikinmu mu din 'yan uwanka ne.''
Ya yi rangaji yana wani abu da hannu kafin ya dumfareta a karo na biyu yana fad'in." Ku ba ni abinda yake hakkina kawai na tafi tunda dama kun sallamawa duniya ni.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR

jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

**Gudun aure paid book complete 2k akan telegram. Normal Gruop wsp 1k via 0542382124... Binta Umar gtbank.*
*07084653262*
*122*
Da farko har ya zauna kusa da ita kamar yadda ta buk'ata sai kuma ya tashi zumbur ya fara d'urawa Rukky ashariya yana fad'in ta daina kallonsa. Anti Yabi ta dinga jan hannunsa tana zaunar dashi yana fizgewa tare da ko'karin zuwa inda Rukky take domin dama can sakuwarsa ce kuma abokiyar fadansa.
Da azama ta d'auki wayarta ta fice daga d'akin cikin tashin hankali don ganin kamar itama yana so ya yi mata lahani.
Yabi ta fara fadin." Babu komai na kudi a d'akin nan Bashir tun daran jiya mun binceke komai sai sutturunta kai kuma namiji ne me za ka yi da kayan mata. 'Yar ta Nusaiba ce ta kwashe duk abinda muke hankoro ta boye sai waccan munafukar Nabila itama tana daya daga cikin wad'anda suka san sirrinta amma saboda ba'kar mugunta ta'ki ba mu goyon baya. Da tun farko ta amince mana da duk haka ba ta faru ba ni kaina a cikin wannan nazarin nake ace an watse ba mu tashi da komai ba."
Nabila na kuka take fad'in." Anti Yabi ba kya ganin abinda ya yi mini lefi ma ki ke ba ni, kina ganin yadda ya yanka min kumatu amma duka baku da damuwa."
Saliha tace." Ke ma kin so haka ta faru Nabila tuntuni muke miki magana kina nuna ke ba ki san komai ba bayan na tabbatar da cewar mukkulin dirowar can yana hannunki mugunta ce ta sanya ki boyewa tunda gashi kina fad'in za ki zauna a gidan. Ina yaran suke da za ki ce zaki kula dasu duk sun zama samari. Su wad'anan 'kananun dole ubansu ya mayarwa da iyayensu Nusaiba kuma ba zama za ta yi ba itama gidanta zata koma, kina so mu tafi sai ki yi wad'aka da dukiya ko to ai duk cikinmu babu yaro mun fahimci me ki ke nufi ."
Yabi ta ce." Tunda abin ya fara zama haka Nabila ki fito da key din dirowar nan nasan anti Maryam a cike take ajiye sirrikanta wata'kila zamu samu gwalagwalanta a ciki da takardun shagunanta da ta mallaka sai mu d'auki wani abu daga ciki mu kasafta a tsakaninmu.."

Cike da damuwa da jin rad'adi ta furta." Ban san inda key din nan yake ba anti Yabi ko ku yarda ko kada ku yarda wallahi ni ma ban d'auka ba. Wayoyinta da ATM dinta suna hannun Nusaiba to key din ma yana wurinta ku je ku binkiceta.
Ya tashi yana rangaji da d'ura ashariya ya fita falon ya ritsa Ruky a zaune domin d'akinsu Mairo ma a rufe yake zage-zagen da yake yi ne ya tashe kaf har da yaran abinda ba su saba ji ba sai kuka. Adam da Salim suka tashi a firgice yayin da Bashir ya dinga bugun kofar d'akin da Nusaiba take kwance da yaranta. Itama a gigice ta tashi tana bud'e kofar ya yi ciki da ita ya ritsata. Salim da Adam suka bi shi d'akin. Itama Rukky ta koma d'aki a guje tana gaya musu gabad'aya suka fito a gigice
Lokacin har ya sa mata wu'ka a wuya wai ta bashi kud'i da mukkulin dirowa an ce komai yana hannunta.
Salim ya yi tsalle ya buga masa duka a bayansa tunda yana tsakiyar Nusaiban ya raba kafufunsa a kanta ya saita ta da wuka.
Gidan ya cika da koke-koke a guje-guje. Mairo da gudu ta ja yaran suka koma d'akin suka rufe. Salim ya d'agata ta shi da gaske ya gilla mata wukar a wuya har ya yi sheda ta matsa gefe tare da ri'ke ma'kogwaronta da ya fara d'an fitar da jini kad'an. D gaske yankar rago ya yi shirin yi mata. Jama'a 'kwaya bala'i ce.
Yaranta ihu kawai suke yi. Nabila ce kad'ai ta iya zuwa wurin da take amma su anti Yabi suna can sun rirri'ke Salim da ya shemar da Bashir din a kasa yana dukan hancinsa.
Da yake ba sosai yake kashe wayoyinsa idan zai kwanta ba. Cikin bacci muka ji kiran waya gabad'aya kusan a tare muka tashi zaune ni dashi ya d'auka da sauri yana sanyawa a kunnansa muka ji muryar Adam cikin rud'u da tsananin tashin hankali yana fad'in." Baba ka zo babu lafiya ka zo yanzu Bashir ne zai kashe anti Nusaiba."
Da wani irin hanzari ya sauka daga gadon na taso na biyo shi ya ce na koma. Har ga Allah na tsorata duk da gidansa cike da tsaro ina jin tsoro ya fita jin ana maganar kisa.
Na koma na zauna cikin tsananin tashin hankali da damuwa wace irin masifa ce wannan kuma.
Lokacin da ya shige gidan Bashir din ya samu nasarar ta shi yana ta kai wa Salim suka da wu'kar da take hannunsa 'karama ce amma kisa da illa take yi nan take.  Ihu da koke ya cika gidan ita Nabila ga yanka a kumatu ga iskokai.
Da hanzari ya nufe shi duk da ya hangi abinda yake hannunsa. Amma da ya gama fahimtar bashi da wani kuzarin kirki irin na maza dalilin shaye-shayen da yake ya dakusar da garkuwar jikinsa sai ya nemi ma'karfafansa ya  kai masa duka a k'irji kafin ya falla masa mari  ya murd'e hannunsa da kyau ya k'wace wu'kar ya mi'kawa Salim ita ya kar'ba duk ya yi wujiga-wujiga ai yayi namijin kokari ma wai aka ce ranar naka sai naka tabbas da da tsautsayi yau Nusaiba zata ba'kunci lahira itama.
Ya ce da Adam maza ya fita ya kira masa Sukairaju da 'Dahuru sune majiya k'arfi sosai fadi yake kisan kai za ka yi mana a gida Bashir dama dan ta'adda ne."

Ya yi shiru yana ciccije baki. Ya dubi Nusaiba dake zaune a gefe yaranta biyu a kusa da ita tana share hawaye sai ya girgiza kansa cike da tsananin damuwa ya kalli Anti Yabi yana jin kamar itama ya falla mata mari, tuntuni ya fahimci bata da hankali gabad'ayansu babu na za'be itama Maryam din da yake shedarta ashe ba'kar macijiya ce.
Tun a d'akin Sukairaju da 'Dahuru suka fara tafkar Bashir ya hana su ya ce dai su caje jikinsa tsaf idan da wani makamin su fito dashi haka kuwa aka yi irin wannan wu'kar uku ce a soke a jikinsa sai daurikan wiwi da ganye ya ce su fita da shi.
Ya juya yana kallon Saliha ita din ya tambaya menene abinda ya faru. Ta fara kame-kame.
Nusaiba tana kuka ta ce." Ba haka ba ne wallahi baba tunda Momi ta rasu suke yi mata bincike d'aki wai tunda sun ji an ce ba su da gadonta. Sun 'ki tafiya ne tunda sun shirya halaka ni, anti Yabi duk abinda Momi ta yi muku da irin abinda za ku saka mata dashi kenan yau kwana uku da rasuwarta kuna rigima har da zubar da jini akan dukiyarta. Ba mu da iyaye wallahi domin ba zamu ta'ba nuna ku a matsayin iyayenmu ba."
Suka yi shiru anti Yabi ta yi kasa da kanta tana fad'in." Ba haka ba ne Nusaiba wallahi kada ki zarge mu domin rashin Maryam na kowane. Ba mu da yadda za mu yi da Bashir tunda ya zo yake daga mana hankali wai a raba gado a bashi rabonsa, amma mu ai mun fi buk'atar Maryam akan abinda ta tafi ta bari na dukiya."
Babu wanda ya ce mata komai, ya sake duban Nusaiba a karo na uku yana fadin." Ya aka yi har ya shigo ya yi miki Illa abinda nake so na ji kenan.
Tana kuka ta ce." Wai sai na bashi wayoyin Momi da atm din da kuma mukullin dirowar da take ajiye muhimman abubuwanta."
Ya gyad'a kansa cike da tsananin al'ajabi da mamaki, shi kaddararsa kenan abokinsa ya rasu ya bar shi da rikicin iyalinsa in ba haka ba shi a tarihin rayuwarsa da family dinsu wani abu na tashin hankali makamancin wannan bai ta'ba faruwa ba.
Ya kama hanyar fita yana fad'in." Zo mu je d'akin ki nuna mini dirowar.
Ta tashi da sauri tare da sanya yaranta a gaba ta bi bayansa su kuma suna tsaye cikin jin kunya Ruky ce kawai take tsugune gaban Nabila tana yi mata tofi.
Madaidaiciyar dirowa ce ta mussaman domin ba irin ta gado ba ce wannan maybe daban ta sanya aka yi mata.
Ya d'an ta'ba ya ji yanayin katakon yana da nauyi. Sukairaju ya kira a waya ya ce ya dawo. Ya fito falon Salim da Adam suna tsaye suna magana ya a kira Mairo. Adam ya dinga bubbuga kofar dakinsu tana fad'in." Wanene a cikin tsoro."
Sai da ta yi muryar Adam din tukkuna ta bude ta fito Taburni ta biyo bayanta duk sun gigice kuma a tsorace suke. Ya ce su had'o kan yaran kaf su biyo bayansa. Haka akayi kuwa yaran duk suka fito ganin Babansu ya sanya suka ruga wajansa suna kuka tunda a gabansu abin ya faru lokacin da Bashir din ke ko'karin kai wa Nusaiba duka ga fuskar Nabila da ta'bon yanka da jini."

Duk da Bashir din baya gidan Nusaiba kasa zama ta yi a gidan dalili ta tsorata ainun da 'yan uwan momin nasu. Salim da Adam ne kawai suka koma dakinsu ita kuma ta bi bayansa da yaranta tana kuka cikin tashin hankali ga wuyanta yana d'an yi mata zugi kad'an dole sai ta je asibiti.

littafin gudun aure na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Haka muka kàrasa kwana cikin alhini da damuwa mai tsananin gaske.
Da safe da wuri Salim ya shigo ya biyo ni har d'aki ya gaishe ni amma bai yarda mun had'a ido ba ya ce mini asibiti za su je yanzu da Nusaiba na biyo shi falon sai na same su tare da maigidan a tsaye suna magana itama ta gaishe ni cikin jin nauyi na amsa tare da tambayarta jikin ta ce da sau'ki.
Sai bayan da suka fita ne tukkuna ya juyo yana kallona tare da cewa." Ina yaran suke?"
Na ce." Suna tare da Mairo a can d'akin Baba Tabawa."
Ya sauke ajiyar zuciya kafin ya ce." Sun dawo gidansu daga yau." Cike da godiyar Allah na furta." Allah Ya taya mu riko ya kuma albarkace su."
Sama ya nufa yana amsawa. Ban bi bayansa ba sai da na kintsa jikina tukkuna na hau na same shi shima ya yi wanka yana dan duba wayarsa. Na ce." A kawo maka abin kari ko?"
Ya ce." Bari zuwa an jima kad'an, abin nan da ya faru ya daga mini hankali Amina, wai me wasu suka mayar da zumunci ne, mutane idonsu ya rufe akan abinda duniya. Yar uwar nan ta su sanin da na yi mata lokacin da take raye ta wahalta musu kwarai da gaske domin ko kafin rasuwar iyayensu itace jigon kula da su Alhaji Amadu na yin nasa ko'karin. Ina daya daga cikin mutanan da suka dinga bashi Sha'awar bata goyon baya tare da ha'baka kasuwancinta tunda iyayenta ba su da k'arfi kuma itace babba. Ta yi musu zumunci k'warai ta kuma dinga ko'karin halakar da kanta duk akan su rayu yanzu ta fad'i ta mutu suna rigima akan abinda ta bari, abinda ya fi ba ni tsoro Bashir da yake ko'karin halaka yarinyar nan Nusaiba akan abinda bashi da hakki."
Ajiyar zuciya na sauke tare da fad'in." Gaskiya da tsoratarwa a cikin wannan lamarin. Jiya da daddare na ji ita Nusaiban tana cewa shi Bashir din ya gudu an neme shi an rasa amma yana jin rasuwar ya dawo wai a bashi hakkinsa."
Dariya ya yi irin ta takaici kafin ya ce." Ba shi da hankali ai da alama shaye-shayen da yake ya fara ta'ba masa kwakwalwa wannan barin irinsu ai babbar masifa ce, yana can hannun hukuma ai dama nemansa suke yi d'an iska."
Na kalle shi jin ya yi zagi tabbacin abin ya yi masa ciwo sosai na furta." Allah Ya rufa asiri yasa mu fi karfin zukatanmu."
A tak'aice ya amsa da "Amin."
Idona ya sauka kan bakuwar dirowar da na ga Sukairaju ya shigo da ita a tun jiya da daddaran. Ganin inda nake kallo ya sanya ya ce." Sun ce wai muhimman abubuwanta na ciki an rasa mukkulin kuma dalilin da ya sanya na ce a d'auko mini ita gabad'aya idan na samu nutsuwa zan sanya a bud'e a

gaban yaran domin su tabbatar da abinda yake ciki na game da dukiyar uwarsu."
Na ce." Hakan ya yi, Allah Ya kawo musu sau'ki ya kuma takaita."
Ya sake amsawa da Amin Yana fad'in." Kafin na shigo yanzu ai na sake shiga gidan tare da ba su umarni kan cewa duk su had'a kayansu su tafi basu da amfani sam gida kuma ba na Maryam ba ne ballantana su yi magana na Alhaji Amadu ne da y'a'yansa, ba su da gurin zama a cikinsa."
murmushi kawai na yi irin na takaici ina mamakin karfin halin wasu mutanan, a ce akan kudi mutum sai ya sarayar da mutumcinsa. Duk kawaici irin na mutumin nan sun 'kure shi yana korarsu Allah na gode maka daka sanyawa iyayena wadatar zucci shima Baba Sule Allah ya taimake ni ya daina ya kama kan sa ganin yana tara surukai.

Da yamma can kira ya shigo wayata da sabuwar number. Da mamaki na daga tare da sallama. Nusaiba na ji tan fad'in." Anti Amina Ina yini."
Na amsa da kulawa ina saurarantа tana fad'in." Na kar'bi lambarki ne a wurin Adam dama zan gaya miki cewa Salim ya wuce da ni gidana bayan mun dawo daga asibiti ana I gobe addu'ar bakwai zan zo sai na kwana idan an yi addu'a sai na tafi."
Cikin nutsuwa da kulawa na ce." To shikkenan hakan ya yi, Allah Ya huta gajiya ya kuma kiyaye faruwar hakan anan gaba. Ita kuma Mominku Allah Ya yi mata rahama."
Ta amsa da "Amin cikin sanyin jiki muka yi sallama.
Koda na gayawa maigidan yadda muka yi da ita yace ai ta sanar da shi.
A daran ranar Mairo da Taburni suka had'o kan kayansu da na yaran gabad'aya kayansu na sanyawa da kayan wasansu irin wanda Momin take saya musu Minal ta dinga bin Mairo tana kuka wai sai ta tashi sun koma gida a daran. Ta'ki jin rarrashi Hassana da Husaina dama babu fuska domin ba su ganta ba a wajena suna zaune dai suna kallonta duk sun yi shiru kamar a tsorace suke da ni. Sun 'ki sakin jikinsu rigima take yi sosai lallai sai Mairo ta tashi sun tafi na kamo ta ina fad'in." Za ki je wurin Baba?"
Ta d'aga kanta. Na dubi Mairo tare da fad'in." Ta ja su d'akinsu da na ware musu a falon su ci abinci. Baba Tabawa ta samu mataimakiya Taburni tare suka shiga kicin a yammacin ranar.
Na ce su yi sallah isha'i tukkuna kafin su ci abincin."
Ta amsa da "To." Wanda ya yi daidai da lokacin da ya sauko ya dubi Khalil yana fad'in." Yi maza ka dauro alwala mu je massalaci."
Ya tashi da sauri.
Ya dube Minal din dake saman cinyata tana kuka. Hannu ya mik'a mata ta sauko daga jikina ta nufe shi ya sunkuya ya d'auketa ya sanyata a k'ugunsa irin d'aukar dai ake yi yaran da ba su wuce shekara biyu zuwa uku ba.
Ta yi shiru tana sauke ajiyar zuciya ya dube ni yana fad'in." Me aka yi mata ne?"
Na tashi tsaye ina fad'in." Wai sai Mairo ta tashi sun tafi gida."
Ya yi murmushi yana cewa." Amina rigima ai a gidan kike."
Na ce." Gidan Momi fa take nufi."

Ya dire ta a kasa ganin Khalil din ya fito ya ce." Momi ai tana can gidanta na gaskiya Amina, ita kuma Minal nan ne gidansu."
Ya kama hanyar fita Khalil ya bi shi a baya da sauri.
Kaina na girgiza kawai na shige d'akina domin gabatar da tawa ibadar.

***
To ranar sadakar bakwai din kamar yadda ya fad'a abinda ya faru kenan bai ma zauna balle a zo a taya shi zaman. Addu'a kawai ya sanya aka yi mata a massalatai. Nusaiba anan wurina ta kwana duk da Nabila tana can gidansu ita bata tafi tana tare da su Salim don bala'i har da kukanta tana fad'in ba zata iya tafiya ta bar su su kadai ba, kuma mamansu kafin ta rasu ta ce ko bayan ranta ta tsaya ta kula mata da yaranta. Haka suka ha'kura suka kyaleta shima Yallabai din da ya ji cewar ba ta tafi ba sai da abin ya bashi haushi sosai ya k:yaleta ne kawai domin ya ga iya gudun ruwanta. Duk da Nusaiba ta san tana gidan hakan bai sanya ta shiga ba nan su Salim din suka same ta. Ta shiga cikinsu Mairo suka yi  aikin funkaso da fanke manyan kuloli aka fita da su domin sadaka.
Tun bayan azahar ya shirya ya fita. Muka kasance da Nusaiba da yaranta har bayan la'asar kafin ta yi shirin tafiya gidanta.

Yana shigowa estate din Sukairaju da 'Dahuru suka yi ram da shi Malam Isiyaku ne Malamin Hajiya Maryam da ya zo kar'bar kudinsa kamar yadda aka al'kawaranta masa.
A mota suka zura shi tare da zuge gilashin motar sai ya fara zare ido na k'aduwa da tashin hankali. Sukairaju ya ce." Maigidanmu ne ya ce mu kai masa kai can gidan hutawarsa za ku tattauna wasu batutuwa ko ba kaine malam Isiyaku ba."
Ya gyad'a kansa da saurin baki ya furta." E, ni ne, Malam Isiyaku."
D'ahuru da yake driving ya ce." To kada ka damu  lafiya za ka fito in sha Allahu."
Ya yi shiru yana zazzare Ido. To ai shi ba haka ake yi da shi ba me yasa za a yi masa kamun kazar kuku  magana aka yi akan mai hakki ya fito ya fadi hakkinsa a ganinsa hakan da aka yi masa tozarci ne tunda shi ba 'barawo ba ne.

Gabansa suka dire Malam Isiyaku da tunda suka isa guesthouse din suka sanya shi a tsakiya babu wata hanya da zai samu ya fece..
Suka fita cike da bin umarni.
Ya dube shi a nutse Yana fad'in." Nutsu sosai ka kwantar da hankalinka. Na buk'aci ke'bewa da kai anan ne saboda muhimmanan batutuwan da zamu tattauna da kai, ai komai yana buk'atar sirri ko."
Ya gyad'a kansa kamar k'adangare kana ganinsa za ka gane a tsorace yake ko ina aljanun nasa suke oho. Wato ashe duk karyar banza ce."
Ya gyara zamansa a gabansa kamar wani mai d'aukar darasi ba malamin da yake da 'kumaji da dulmiyar da al'ummar annabi ba."

Ya ce.'' Tun sanda ka ba ni labarin abinda yake tsakaninka da Maryam mai rasuwa na gaza samun nutsuwa da kwanciyar hankali, a takaice nake sanar da kai har ciwo na kwanta saboda tsananin tashin hankali da damuwa. Malam Isiyaku shin za ka gaya mini irin bak'aken  ayyukan da aka yi wa Maryam domin zalinci. Kada ka kuskura ka 'boye mini komai nasan ni ma da nake zaune nan a gabanka ka yi aikina ai asiri da tsafi gaskiya ne tunda ya ci annabinmu fad'in gaskiya shine abinda zai k'waceka bayan haka kuma ina so muje da ni da kai a gabana duk inda kayi binne a kaina ko akan wani na ka tone shi da hannunka."
Ya ki'dime sosai da sosai ya kasa zama Yana fad'in." Yallabai Wani aikin kaikayi ne wallahi idan na karya shi zai dawo kaina, zan iya kwanciya ciwo ko abin ya shafi iyalina don girman Allah ka gafarce ni."
Ya dube shi cike da tsantsar mamaki ya ce." Abin zalinci ne kenan, me yasa gabad'ayanku baku da imani ne, kai kanka kana gudun kada abinda ka yi ya shafi iyalinka to me yasa ka yi. Okey shikkenan tunda duk ina da bayanai a kan ka zan had'a ka da hukuma su za su yi maka tonan asiri duniya ta sheda wannan rawanin daka nad'a a kanka na zalinci ne furfurar dake gemunka kuma ta banza ce, daga nan 'yayanka da kake gudun su damu lahani su yi tur da kai da nadamar fitowa daga tsatsonka."
Ya ce." Duk ba za mu kai ga haka ba ranka ya dad'e za mu je duk inda na yi haka da binne a kanka zan tone da hannuna in sha Allahu ko da hakan zai zama barazana ga rayuwata."
Ya gyad'a kansa yana kallonsa cikin nazari kafin ya ce." Maryam ta yi aiki a kaina da iyalina kenan.''
Ya rusanar da kansa yana fad'in." K'warai kuwa na yi mata aiki akanka da kuma tsohon mijinta Alhaji Amadu akwai wanda na yi binne a kasan bishiyar kuka akwai wanda na yi a bishiyar tsamiya da kuma d'aurin baki  da aka yi maka shima yana can za mu je ka gani domin laya ce aka 'dora mata gungumen dutse a can cikin wani daji.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *Gudun aure paid book 2k complete on telegram what'sapp Gruop 1k via 0542382124...... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*123*
Wato a duk lokacin da Ubangiji ya so bawansa da rahama ya kan wanke shi ya daidaita tunani da tafarkinsa zuwa hanyar tsira ya kuma yafe dukkunanin kuraransa. Allah," Ya ce kada ku hada ni da wani bawa na wurin neman biyan buk'ata ni ne da Ubangijin talikai mai jin kai, mai kuma bayarwa da hanawa. Ni ne d'aya wanda ba ni da farko da kuma k'arshe. Ku ro'ke ni da kowane irin yare ina jinku zan kuma amsa muku.
Had'a Ubangiji da waninsa babban zunubi ne da yake tabbatar da cewa babu afuwa da yafiya daga wajensa. Domin Allah yakan iya yafe kowane irin zunubi ne mutukar bawa ya yi tabbaccen tuba.

'Kwarai da gaske ya girgiza ya kuma shiga razani da nadamar rayuwa a lokacin da suka dinga haurawa kan dutse tare da Malam Isiyaku da yaransa biyu Sukairaju da D'ahuru. Duk gwagwarmayar rayuwar da ya yi ta duniya k'afarsa bata zuwa ire iren wannan wurin ba. Karamin gari ne a cikin jos din kuma mafi akasarinsu maguzawane. A wannan 'kauyen da mahukunta suka manta dashi nan Malam Isiyaku ke zuwa ya gudanar da ayyukansa. Tunda a bayan gari yake kuma gari ne da ba su san menene addini ba.
Suka dinga tsallake koguna da dutsina suna wuce manyan bishiyun kuka masu tsananin firgitarwa da bada tsoro.
Wata narkekiyar bishiyar kuka suka nufi mai manyan koguna kuma babu ganye a jikinta.
Suka tsaye gabad'aya wurin tsit sai kukan tsinye-tsinye ne ke tashi. Da alama bishiyar ta zama sansani wurin ajiye kayan asiri domin ga layu nan birjiki wasu a cikin kwalabe wasu kuma an nad'e su da jan zare da kwalaban tururukan da iska ke so.
Ya tsuguna ya fara wasu zantuka kimanin minti goma ya gama can daga gefe ya fara hak'a da zurfi sosai ya d'auko wata doguwar kwalba da ta fara rinewa cikinta cike da allurai da bakin yadi mai kama da likkafani a ciki. Daga 'kasan wurin da ya yi hak'an ya cire yadin likkafani shima ya dan rine da kasar wajan Amma hakan bai hana ganin sa'kandamin da yake zane ba.
Ya taso da kayan a hannunsa yana fad'in." Na ha'ko nan."
Ya tambaye shi nasa ne ko na Alhaji Amadu. Cike da nadama da tsoron abinda zai biyo baya ya ce." Na ka ne Yallabai."
Ya ce ya warware a wurin. Sukairaju da ba shi da tsoro ya kar'bi likkafanin da sa'kandamin yake hannunsa suka fara dubuwa.
Zanen hotonsa ne tsaf kowace ga'ba da kusurwa ta jikinsa rubuce da sunan Allah da kuma wani irin jagwalgwalon rubutu mai ri'ke ta kwakwalwa. Abin mamaki yadin likkafin yana ta 'kamshin wani irin turare mai masifar karfi.
Ya dube shi yana fad'in." Menene makarin aikin."
Ya ce." An karya ai tunda an ha'ko."
Suka yi gaba bishiyar tsamiya ce itama turgijejeya kana kallon wannan bishiyasa zaka tan ta tara 'kwan'kwamai masu illa gashinan ma da kanta take kamawa da wuta tsabar sansanin bak'aken aljanune.
Itama dai kamar daya bishiyar kukan aikin mutane ne birjik a k'asanta da sassan reshenta tunda akwai ragowar ganye a jikinta ga layu nan murtuka murtuka suna ta reto wasu daban wasu a cikin kwalabe."
Ya shiga mamaki sosai da ya ga ya d'ane bishiyasar can k'ololuwa ya kamo wani reshe ya d'auko wata doguwar kwalba da aka d'aureta sosai a jikin reshen an nannad'eta da jan yadi ya daddafo ya sauko da ita a hannunsa.
Sukairaju ya mika masa babbar rigarsa yasa yana fad'in." Wannan shine na alhaj Amadu mai rasuwa."
Ya buda kwalbar a wurin ta fashe. Layu k'ananu ne soke da allurai suka fito da wani irin warin turare mai gigitarwa..
A wurin ya sanya shi ya warware layun gabad'aya sunan Allah ne gashinan muraran Maliki yaumiddin mimun din da sunan Alhaji Amadu da Hajiya Ayya babarsa da kuma mahaifinsa. Duk ya warware guda ukun.

Ya bawa Sukairaju umarnin tattarawa ya zuba a leda domin babu damar barin su a wurin da sunan Ubangiji.
Suka yi gaba sosai suka riski wani shuri zungurere ya tsaya a sanyaye yana fad'in" Sati uku da suka wuce na zo na yi aikin wata mata a nan itama akan abokiyar zamanta ne farra'ku zan cire." Ya fad'a a sanyaye da alamar nadama a tare da shi.
Suka tsaya kuwa ya tsuguna ga rana ta kwalle a wurin tururuwai masu yawa sun fito har suna bin kafafunsu. Ko alama bai sare ba, kuma bai tsorota duk da akwai razanarwa saboda ya san jahadi ya yi shiyasa ya fi yarda su je ya gani da idonsa domin tabbatar da duk ya warware kullin da ya yi."
Ya haka gefen shurin inda ya san ya yi ajiyar ya d'auko wata yar tukunya ta 'kasa nan nad'e da likkafani ya kwance layu ne uku masu kauri ya warware cikinsu gashi ne da barkono tsidigu a hade da kuma d'anyan nama wanda kwance layun ke da wuya wari ya game hancinsu. Daga kansa ya yi musu bayani cewar naman na ja'ba ne sai gashin matar da aka yi wa asirin tsidigun (barkono) kuma shi zai dinga zafafawa ma'auratan zuciyoyinsu su ji sun tsani kansu da zama da juna.
Suka gama da wannan suka sake nausawa sosai wannan karon tafiyar da suka yi tafi ta baya can suka riski murgujejen dutsan. Suka tsaya cikin ransa yana raya da wannan aka danne masa baki kenan.

Gudun aure paid book ne kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba

Daga can gefe Malam Isiyakun ya tsaya ya takarkare yana ture dutsen D'ahuru ya taimaka masa. Aikuwa sai ga wata laya mai fad'i a kwance tsabar nauyin dutsin ya sanya ta tamushe duk tudunta da nannad'ar da aka yi mata.
Suka d'auko tare da fara kiciniyar kwanceta yana tsaye yana kallonsu jikinsa duk ya yi sanyi wato nan aka kawo bakinsa aka daure to akan me wai? Annabi ya yi gaskiya da yake cewa mata za su kasance da yawa a wuta, shi kam bai ga abinda ya yi wa Maryam ba da za ta yi masa haka.
Aka warware laya itama mai cike da sa'kandamai guda uku daga kowane sashe sunan da labaraci ya fito radau Tajudden!.
Suka had'a kan komai suka juya da baya domin fita cikin gari.
Sukairaju da D'ahuru suna bayansu shi da Malam Isiyaku suna gaba.
Ya d'an dube shi da gefan Ido gabad'aya ya yi sanyi mutumin fargaba ta mamaye shi. Tausayi ya bashi kad'an domin dai babu yadda za a yi ya sake shi ba tare da ya sanya hukuma a ciki ba. Mutumin banza ne wanda zuwansa duniya bai amfanar da kowa ba. Abin jajantawa da tausayawa iyalinsa da ya jefa rayuwarsa cikin gagari da 'kyama ta jama'a duk da akwai ire-irensa da yawa a gari masu ci da addini da halakar da mutane amma a ganinsa wannan nasa ya yi muni sosai.
Ya ce." Ranar da ka fara yi mini bayani akan za ka yi aiki akan matata Hauwa ita dayar ba ka ta'ba wani aiki a kanta ba?''

Ya yi shiru na d'an wani lokaci kafin ya furta." Idan itace Amina gaskiya marigayiya bata ta'ba sanya ni aiki a kanta ba, abinda na sani shine ta ta'ba ce mini tana so a had'a taurarinta dana Amina din saboda nata suna da haske sosai kuma iyayen makarai ne a tare da ita tana da jalabi sosai bayan haka ma ba kasafai jifa ya ke kaita kasa ba tunda ba raguwa ba ce wurin addu'a. Taurarinta suna da tsananin haske dalilin da ya sanya kenan itama ta buk'aci da su yi musharaka wurin haduwar taurarin.
Ya jima yana girgiza kansa da mamakin abin. Ya jima da sanin cewa ana iya amfani da haske da taurarin mutum domin cimma wata manufa wasu lukutan mutum na zaune kaf sai a kwashe masa taurari bai sani ba. Wato malam ka ji tsoron Malaman yanzu da suka kwashe kayansu daga gaban ma'aki.

Kwana da yini suka yi a garin jos duk yadda Malam Isiyaku yake karyar da kai da nuna ya yi nadama bai saurare shi ba. Yana da jama'a sosai duk da wata mu'amula ba ta ta'ba had'a shi da shugaban jami'an tsoron garin ba. Dalilin suna da shahararsa a duniya ya sanya a daran ya gana da commissioner yan'sanda suka cika hannu da  Malam Isiyaku zuwa sansaninsu.
Gajiya kam sun kwaso ta daga shi har yaran nasa ga tafiyar mota sai gefen asubahi suka shiga garin abuja ana ta kiran sallar farko.

Ban san ya dawo ba sai da gari ya waye tukkuna na fito na same shi da yaran gabad'aya a falo a zaune. Sun zagaye shi yana ta sauraransu yana murmushi Minal yar lelanshi tana kan cinyarsa. Twins kuma na gefansa a tsaye suna ta tsalle Khalil na saman kujera a zaune. Dukkaninsu cikin tsafta Mairo ta kintsa su. Suna ta 'kamshi.
Na yi murmushi ina kallonsu gwanin ban sha'awa na ce." Cikin dare ka dawo ne?"
Suka juyo gabad'aya suna kallona har da shi ba su lura da fitowata ba sai da na yi magana.
Ya gyad'a kansa a nutse ya ce." Gefin asuba na shigo Amina. Ya kuke na same ku lafiya."
Na ce." Alhamdulillahi ya su Hajja?" Domin ni ce mini yayi kano za shi kuma zai kwana daya."
A tak'aice ya furta suna gaishe ku."
Ya sauke Minal kasa Yana fadin." Zan kwanta zuwa an jima ki tashe ni."
Na ce." To shikkenan."
Ya haye sama da dan sauri.
Na dube su Usai ta yi saurin janye idonta daga kaina. Na sassauta fuska tare da mika mata hannuna ina fad'in." Zo." Tun ranar da na mur'de mata kunne take ja baya dani. Hassana ce ke iya zuwa kusa da ni har ta yi mini hira. Minal kuwa yar d'akina ce tunda ita dama can akwai ta da saurin sabo."
Ta zo din kamar yadda na buk'ata amma bata kalle ni ba.
"Na ce." Menene?"
"Babu komai."
Na ri'ko hannunta a nutse na furta." Kina jin tsorona ne?"

Ta girgiza kanta. Na d'ora ta saman cinyata ta ai kuwa sai tasa dariya tana kallona abin ya zo mata daban.
Hassana ta taho itama tana bata rai. Na dauketa na sanya a daya gefan suka dinga dariya suna yi wa Minal gwalo ita kuwa mai neman jiran kiris ta fashe da kuka. Khalil yana yin dariya ya ce ni zo na goya ki."
Na ce." Zo nan goyo kike so ko?"
Ta daga kanta. Na ce." To ta kwana gidan sau'ki je ki ce Mairo ta bada abin goyo."
Ta kuwa ta fi da sauri.
Na dire su a kasa ina fad'in." Idan ba ku sanyata kuka ba bakwa jin dadi, kun yi girman banza."
Ina shiga d'aki ta shigo da towel din Sultan tana mika mini na ce." Aiki ya same ni kenan, gashi wanka zan yi yanzu Minal amma muje."
Ta biyo bayana na samu Taburni da yaran tana had'a musu tea na ce." To zauna ki ci abinci idan na yi wanka na fito zan goya ki."
Mairo da ke goge musu kayan makaranta ta ce." ashe da gaske goyon za a yi Hajiya."
Na ce." K'warai kuwa Mairo na juya na fita daga d'akin ina jinsu suna yi mata dariya.
Na sami Adam a falon a tsaye wanda shigowarsa kenan. Muka gaisa yana tambayata Baba ya dawo?"
Na ce masa ya dawo amma ya kwanta sai zuwa an jima ya dawo lokacin ya tashi.
Ya ce to cikin sanyin jiki kafin ya juya ya fita na bi shi da kallo gwanin ban tausayi.
Wajan daya da rabi na tashe shi domin yin sallah.
Ya tashi zaune yana kallona goye da Minal a baya. Ya ce "Wacece a bayanki?"
A tak'aice na ce." Name sake dina ce."
Sai ya yi murmushi ya ta shi ya shiga bandaki ina zaune ya fito d'aure da alwala na ce." Adam kuwa ya shigo nemanka d'azu."
Ya ce." Zuwa an jima zan nema shi. Sallah zan yi yanzu ki kawo mini abinci.".
Na tashi na sauka kasa na had'o masa abincin da abinda zai buk'ata na koma na same shi ya idar amma yana gyangyadi a saman daddumar hakan kuma ba dabi'arsa ba ce.
Na ajiye tiran ina tashinsa ya tashi ya nufi bed yana fad'in." Baccin zan sake komawa.
Da mamaki na ce." Abincin fa.''
Ya rufa da bargo  yana fad'in." Sai na tashi tukkuna.
To wasa-wasa haka ya wanzu tsayin kwanaki hud'u yana wannan baccin gabad'aya yin ibada ne kawai yake tashinsa idan ya gabatar ya ce zai koma ya kwanta da rigima sosai yake cikin abinci ya zama kamar wani sususu jikinsa babu kuzari sai bacci sai kace wani rik'akken d'an 'kwaya.
Hankalina ya fara tashi domin na ce masa ya kira likitansa ya duba shi bashi da lafiya ya ce na kyale shi a hankali zai warware kawai dai na cigaba da kunnansa karatun al'kurani. Ganin abin nasa ya'ki sau'ki na fara kuka domin

tunda ya yi tafiyar nan ya dawo bai kwanta da ni mun yi sunna ba kwana biyar yanzu wanda a tarihin rayuwarmu  hakan bai ta'ba faruwa ba.
Muka dinga rigima akan na ce zan gayawa Hajja ba shi da lafiya a ganina ai mai matsalar aljanu da farfadiya ya kamata ace ana kunnawa akaratun al'kur'ani a saitin kunne, ga yanayin jikinsa ya nune babu kuzari amma ya ce shi lafiyarsa lau wace irin gajiyace wannan da zata mayar da shi d'an maye kullum bacci....✍

*BINTA UMAR ABBALE*

https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*

*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*
*Gudun aure paid book 2k complete on telegram what'sapp Gruop 1k via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*124*
A cikin kwanakin da ya kasance cikin wannan yanayin ki'ba ya yi ta fuska sosai ban sani ba ko baccin da yake yi ne ya janyo faruwar hakan oho! tunda gaskiya ba abincin kirki yake ci ba ballantana na ce tun asali ma mutum ne shi da bai fiye tasa abinci a gaba ya yi ta narka ba, kuma ba shi da irin ciye-ciyen nan na masu kudi.
Cikin dare na tashi na yi sallah raka'a biyu na tsananta addu'a sosai domin abin ya fara daga mini hankali yanzu kuma na gano babu shakka akwai abinda ya faru wanda yake b'oye mini.
Gefan kansa na zauna na bud'e alk'uranin izifi sittin din da yake hannuna daga sama na fara a cikin nutsuwa har aka fara kiran sallar farko wanda ya yi daidai da lokacin ya motsa. Ya tashi zaune yana kallona na rufe al'kur'anin muka dubi juna na dan wani lokaci kafin ya kira sunana na amsa.
Sai ya zura k'afafunsa kasa domin sauka yana fad'in." An yi kiran sallah ko?''
Na ce." Za a yi yanzu dai."
Toilet din ya nufa na bishi da kallon nazari kafin na tashi na bi bayansa na ga yana had'a ruwan zafi dana sanyi wanka zai yi ban hana shi ba kawai na ja masa k'ofar na fito na zauna har ya kammala ya fito d'aure da towel ashe ba iya fuska ya murmure ba har jikin gabad'aya.
Ga mamakina da kuzarinsa ya kintsa ya fita massalaci wanda ya d'auki kimanin kwanaki biyar rabon da ya sanya kafarsa a waje duka sallolinsa a gida yake yin su ya koma ya lafke a gado.
Kasa sauka 'kasa na yi har sai da gari ya yi haske ya dawo. Ya gan ni a zaune bai nuna mamaki ba na zuba masa ido har ya zo ya zauna kusa da ni wanda na yi zaton kwanciyar zai sake yi sai naga akasin haka muka gaisa ya ce mini na d'auko masa Loptop dinsa dake ajiye can wurin da yake zama. Cike da jin dad'in ganinsa a haka na tashi da azama na je na d'auko masa har ya bud'e ya kunnanta sai kuma ya kashe ya janyo ni jikinsa.
Ga mamakina na ga yana ko'karin cire mini hijabin dake wuyana.  Muka kalli juna ya kanne mini ido cikin wata kalar murya ya ce." Mu 'dan yi wani abu ko."
Kasa ce masa komai na yi domin ni hakan ma jefe ni ya yi a farinciki ganin ya fara dawowa hayyacinsa. Na biye masa kimanin minti talatin muka d'auka kafin komai ya kammala.
Ya riga ni yin wanka ko da na fito sai na same shi yana yin waya na ji yana kiran sunan wani Malam Rabi'u akan zai tura masa da abin sadaka a sake yin saukar al'kur'anin da aka yi a watannin baya.
Sai da suka gama tukkuna na sake gaya masa Adam ya shigo jiya da shekaran jiya wurinsa.

Yana sake ko'karin kunna Loptop din a karo na biyu ya ce." To zan neme shi na ji menene nasan ba zai wuce maganar Nabila ba ita take turo shi wai zata zauna tare da su."
A tak'aice na ce." Hakan yana da kyau ai."
Na tashi na sauka kasa domin had'a masa abin kari.
Kafin na shiga kicin din d'akin yaran na fara dubawa duk sun yi shirin tahafiz yau asabar da lahadi tun takwas na safe suke tafiya sai shida. Ranakun da suke da boko kuma suna shiga k'arfe uku. Dukkaninsu cikin uniform a tsaftace kamar yadda dai suke yi musu hidima a gidan Momin Taburni da Mairo kowanne da lunchbooks dinsa. Ganinsu ya saukar mini da wata irin nutsuwa da kwanciyar hankali a raina na tsinci kaina cikin nishadi da annashuwa suka fara gaishe ni ina amsawa tare da tsokanar Minal yau sai makaranta.
Falon muka fito tare na ce." Mairo ta kira mini Masa'udu. Kamar yadda suka bar gidan Maryam ba ni son abinda zai sake dangantasu da gidan duk kuwa da cewa direban da yake jigila dasu yana nan tare da masu gadin amma ba ni son abinda zai sake kai yaran gidan ina so su fara gina sabuwar rayuwa mai cike da nutsuwa da kwanciyar hankali.
Ya shigo tare da risinawa yana gaishe ni na amsa na ce.'' Daga yau za ka cigaba da kai yara makaranta kafin Babansu ya samar musu da sabon direba."
Ya amsa da "To shikkenan in sha Allahu Hajiya."
Ya tasa kan su gabad'aya har Khalil suka fita suna yi mini bye-bye Mairo ta bi su da jakkunansu da kayan abincinsu.
Na leka d'akinsu Baba Tabawa muka gaisa sosai suna tare da Taburni da alama ta su ta zo daya tunda duk dattijai ne. Sultan na ta bacci cikin net din shi sun shirya shi tsaf.
Har na juya zan fita Baba Tabawa ta ce." Hajiya Amina kina jin mu da Taburni ko wai tafiya gida za ta yi."
Na juyo da sauri ina fad'in." Me yasa Taburni ko an yi miki wani abin ne? ko kuma ba ki jin dadin zama da mu."
Ta girgiza kanta tana fad'in." Ko daya wallahi Hajiya ina so na je na ga yarana da iyalinsu idan hali ya yi zan dawo suna can suna jirana tunda sun san uwar rikon nawa ta rasu wasu daga cikin iyalina ma sun zo gaisuwa."
Na ce." A a gaskiya ba za ki saki aikinki ba Taburni za ki zauna da mu in sha Allahu a madadin marigayya kuma za mu ninka miki albashinki, zuwa ganin gida wannan ba lefi ba ne, amma ina jin dad'in ganinku a tare ga yara sun saba daku."
Kwalla ta cika kwarmin idonta tana fad'in." Shikkenan Hajiya Amina na gode sosai Ubangiji Allah ya saka muku da alheri cikin satin nan zan je na dawo."
Na ce." Zan sanar da maigidan in sha Allahu nasan zai sanya a aiki kuma aje a dauko ki."
Na fita daga d'akin cikin nazari. Idan Taburni ta tafi baba Tabawa ba zata ji dad'i ba sun saba ga yaran ma idan Mairo na wani uzuri wajanta suke zuwa kuma macace mai hankali.

da kaina na shirya masa abinda zai ci farfensun kifin na sake yi masa tunda na ga ya yi masa dadi kwanaki na hada masa da funkaso da tea wanda nasan dole zai bukace shi domin dumama cikinsa.
Ya kuwa ji dad'i sosai kuma ya ci da yawa ya dinga yi mini godiya ina jin dadi a raina ganinsa ya fara nutsuwa har ma yana ta rage ayyukan da ya jima bai yi ba.
To shi din ma da na gaya masa cewa Taburni za ta koma garinsu bai bada goyon baya ba ya ce yara sun saba da ita sosai idan har ba a takura mata ba to na gaya mata ta zauna zai dinga biyanta fiye da yadda tsohuwar uward'akinta take biyanta.
Yinin ranar haka na yi shi babu komai a cikina domin duk abinda na tunkara da zumar kaiwa bakina zan ji zuciyata na tashi abu mai tsami tsami shi na fi sha'awa tun da na fara jin haka kuwa akwai matsala daf nake da yin al'ada idan ba ta zo ba kuwa ciki ne.
Duk yadda na kai ga daurewa kuwa kasawa na yi domin da daddare  amai na dinga kyalayawa Allah ya sa a d'akina ne na yi na gama na gyara toilet din na fito na kwanta lamo cikin kasala sallar Isha'i ma a zaune nayi ta saboda yadda jikina ya mace lokaci k'an'kani.
Sai wajan goma da arba'in na dare na iya fitowa falon shiru yaran duk sun shiga sun kwanta. Na nufi saman abin mamaki hawa daya biyu zuwa uku sai da na zauna na huta. A haka na kàrasa hayewa zuwa d'akin nasa.
A bud'e yake tunda dama yana tsammanin shigowata na same shi yana waya da harshen larabaci karo na biyu kenan da na ji shi yana magana da harshen. Ranar da aka d'aura auranmu a makka da kuma yau. Ban jima da zama a gefansa ba ya gama wayar ya dube ni yana fad'in." Hajiya yau mantawa ki ka yi da ni ne?"
A tak'aice na ce." A a gani na yi ka ji sauki ai."
Ya ce." Sai ba ni da lafiya za ki zo wajena har ki d'ora kaina anan." Ya fad'a tare da dora hannunsa saman kirjina.
Murmushi kawai na yi ban ce masa komai ba kaina ne ma yake yi mini ciwo.
Ya ce." Tunda magriba da ki ka kawo mini abinci ki ka sauka ba ki dawo ba ko na yi wani abin ne?"
Ya fad'a cikin rausayar da kai."
Na ce." Babu abinda ka yi kawai na ga kana aiki ne shine na ce bari na dan baka wuri ka kammala."
Kira ya shigo wayarsa ya d'auka na ji yana fad'in." Lafiya ya kike ina Uwani."
Daga nan na fahimci Hauwa ce. Sai na juyar da kaina gefe to da yake hands free wayar take na ji tana fad'in." Yau kwana uku Ina neman wayoyinka bata shiga."
A tak'aice ya ce."
"Ba ki da number Amina?" Ya bata amsa da haka.
Ta ce." Itama ba ta shiga."
Da mamaki na kalle shi wayata kullum a kunne take wannan ba gaskiya ba ne ba ta kira ni ba.
Ya ce mata." Ok
Ina fatan lafiya ko?"

"Ba ni da lafiya ne?" Ta fad'a cikin 'yar k'aramar murya."
Babu wani gigita a tare da shi ya ce. Sannu idan kin je asibiti sai ki sanar da ni abinda ya kasance na sayan magani zan sa miki."
Daga haka bai jira jin abinda za ta sake cewa ba ya datse wayarsa ya ajiye.
Ya dube ni muka had'a Ido sai ya kanne mini idonsa yana fad'in." Ina labari?"

Gudun aure paid book ne yar uwa kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na ce." Kai zan tambaya domin cikin kwanakin nan ka jefa ni cikin rudani"
Ya sauke ajiyar zuciya bai ce komai ba sai ya d'ora kansa saman tudun kirjina. Ni ma da taya 'bera 'bari na tallafe masa kan ina shafa shi. Ai sai na kunna shi ya sake ma'kale ni tare da zura hannuwansa duka biyun ya kewaye 'kuguna. Mun jima haka Ina ta shafa saman kansa a hankali yana ta sauke ajiyar zuciya babu wanda ya sake yin magana a cikinmu. Hauwa ta sake kiran waya a karo na biyu ba tare da ya d'auke kansa daga kirjina ba ya d'auki wayar yasa a kunnansa. Ta fara maganar da karamin sauti ban ji komai ba, ni kuma daman ban so na jin ba na ji yana fad'in." Babu halin hakan."
A tak'aice ya gaya mata haka duk kuwa da cewa doguwar magana ta yi masa ya sake dai kashe mata wayar a karo na biyu na ji shi can kasa yana fadin." Na d'auka mutuwa zan yi a cikin kwanakin nan ban zaci zan sake moruwa ba wallahi saboda tsabar yadda ga'bobin jikina suka mutu."
Na ce." Ni ma na tsorata gaskiya amma dai duk da haka yana da kyau likitanka ya dubaka sosai baka da lafiya."
Ya ce." Hakan za a yi in sha Allahu." Ya d'auke yana gyara zamansa na ce.'' Kasan yaran nan sun koma makaranta yau ko?''
Ya ce." K'warai kuwa mun yi magana da Masa'udu d'azu dana fita sallar la'asar zai maye gurbin Dauda direbansu na can gidan Maryam."
Na ce." Hakan ya fi."
A daran ranar ma sai da ya yi auratayya da ni, na dinga daurewa domin akwai buk'atar hutu da samun bacci a tare da ni ga jikin babu kuzari. Sai da ya gane kuwa ya d'an saurara mini da asuba da yawo daga massalaci bai sake nema na ba.
Nima tunda na koma bacci bayan sallar asubahin ban tashi ba sai wajan sha biyu da kwata sai da na yi wanka tsaf na kintsa jikina sannan na fito yaran suna makaranta a falon na samu Mairo da Nusaiba suna hira Taburni da Baba Tabawa suna kicin suna aiki.
Cike da girmamawa duka suka yi mini barka da fitowa na nemi wuri na zauna cikina na hautsinawa yunwa da tashin zuciya bakina salam. Ina fad'in." Yaushe ki ka zo ne?"
Da murmushi a fuskarta take fad'in." Wajan sha daya da rabi Baba ya kira ni yana sama amma bai sauko ba mun dai yi magana a waya ya ce mu jira shi."
Na ce." Allah sarki Ina yaran na gan ki ke kadai."

Ta ce." Suna makaranta anti."
Salim da Adam suka shigo cikin kaya iri daya gabad'aya yaran daga lokacin rasuwar Mamansu zuwa yanzu sun ladabtu sosai ba kamar Salim da yadda yake risina mini ke ba ni mamaki yaron da ya d'auki mummunan gaba da ni. Itama Nusaiban har yanzu bata iya had'a Ido da ni. Adam kuwa dama d'an d'akina ne tunda suna tare da Yusi.
Muka gaisa cikin kulawa na tashi ina fad'in." Bari ina zuwa."
saman na nufa  domin sake sanar dashi zuwan yaran. Sai na same shi shi da Sukairaju suna ta kicin-kicin bud'e wannan dirowa da aka shigo da ita kwanakin da suka shige.
Da kyar suka samu nasarar bud'eta da dabaru da kuma wasu mukkulai da na gansu a hannun Sukairaju...
Na ce." Nusaiba da 'yan uwanta sun zo wajenka."
Bai ce mini komai ba sai da Sukairaju ya fita tukkuna ya fura." E, wannan ma'ajiyar ta Mamansu zan bud'e a gabansu.
Ya d'auki wayarsa ya kira Nusaiban ya ce mata su haho saman.
Muna zaune suka shigo gabad'aya suka gaishe shi ya amsa cikin kulawa yana tambayarta yara da yanayin jikinta. Ta nuna masa wuyan nata tana fad'in." Wurin ya warke alhamdulillahi.
Ya ce." To alhamdulillahi kamar yadda na gaya muku cewa idan na samu nutsuwa sosai zan bude wannan ma'ajiyar domin ni daku muga abinda yake ciki ma sha Allah cikin ikon Allah yanzu Sukairaju ya samu nasarar bud'eta don haka ku ba ni hankalinku gabad'aya.
Ya sanya hannu a nutse zai bud'e
na fara ko'karin tashi domin ba su waje ya ce na zauna. Ba don raina ya so ba na zauna din

Tana da d'an zurfi amma ni da nake zaune kusa da shi na gama ganin duk abinda yake ciki.  Da saurin gaske na d'auke kaina gabana na wani irin fad'uwa.
Daga b'angaransa ban hangi wani razani ba da da hannunsa ma ya shiga fito da abubuwan da suke ciki. Farko dalar amurka ce ta fi bandur ashirin ya gama fito da su sannan ya kwaso tarin akwatinan gold's dinta kusan set biyar manya ba k'ananu ba bayan zobuna na tsayun hannu dake cikin akwatinansu.
Ya debo wasu takardu ya mi'kawa Salim yana fad'in " Duba nan ka ga menene.  Ya kar'ba da sauri ya fara dubawa. Abubuwa biyu da suka yi saura cikin dirowar ya d'auko
Mutumin-mutumi ne mai d'auke da suffarsa da suffarta tsirara kammaninsa sak haka zalika itama kammaninta sak an had'e su waje daya an matse sosai da farin likkafani da jan zare aka nannad'e sannan 'kasa da sama duk an kulle da ko'ina da kwa'do. (Key)
Sai wata kwalba doguwa mai kama da ta lemo cike da turare mai maiko da k'ananun layu a ciki kimanin takwas kowacce soke da allura.

Ya dubi Nusaiba da ta gama kidimewa ganin abinda ya biyo bayan dukiyarsu da Mamansu ta boye musu ya nuna mata yana fad'in." Wannan shine abinda ya rage cikin wannan dirowa Nusaiba."
Sai ta rushe da kuka tana 'kunshe bakinta da hannu hawaye suka fara kasa tsere a kumatunta.
Adam kuwa sunkuyar da kansa kasa ya yi yana cike da damuwa mai yawa.
Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un kawai take fad'in tana kuka. Shi kuma Salim sakato kawai ya yi da takardu a hannu ya tsirawa abubuwan ido yana kallo cikin jin nauyi da kunya.
Ganin yadda duk suka ki'dime ya sanya ya fara rarrashinsu yana fad'in su nutsu Nusaiba dai fadi take yi don Allah Baba ka rufa mana asiri ka ce ka yafe mata ko zata samu rahama. Anti Amina kuma don Allah ku yafe mata ban sani ba ko ta yi muku wani abin na cutarwa ni dai wallahi ban san Momi tana bin wannan hanyar ba domin kullum idan mun zauna da ita cikin yi mana fad'a da nasiha take bantaba sanin abinda take yi ba."
Ya ce." Babu komai ku nutsu kowane dan Adam yana tare da jarrabawarsa a duniya mai kyau ko mara kyau ni daku duka ba mu san abinda yake lullube ba domin alherinta muka sani shi kuma muka dinga fad'a bayan mutuwarta. Ba ni da masaniyar cewa ta tuba kafin Allah Ya d'auki rayuwarta tunda zuciyarta a kirjinta take kuma ba a bud'e mini na gani ba. Na yafe mata Ina kuma roka mata sasaauci daga mahallicinta. Wannan abin da kuka ga ni zai zama sirri in sha Allahu, abinda nake so daku gabad'aya shine ku samu nutsuwa kada cikinku wani ya sanya damuwa a ransa. Ina nan har yanzu a madadin mahaifinku kamar yadda ya ba ni amanarku in sha Allah......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

*Paid book ne 2k complete on telegram WhatsApp Gruop 1k 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
Kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba. Mu kiyaye mu kula da hakkin junanmu.
Kukan da Nusaiba take yi shi ya fara ta'ba mini zuciya na ji hawaye ya cika kwarmin mini idona. A hankali na janye idona daga kanta gabana na fad'uwa cikin raina ina ta kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! Yadda yaran nan suka ki'dime ganin abinda Mamansu ta mutu ta bari na sa'bawa Allah shine ya tabbatar mini da cewa duk zargin da ake yi mata na cewa mushirikiya ce ba su gazgata ba sai yanzu da mutuwa ta yi mata tonan silili. Babu kama ko d'aya a zahirance da kuma mu'amularta domin ni kaina ban ta'ba gazgata maganar dake yawo a kanta ba saboda ban ga ni da idona ba a wasu lukutan dai idan abin ya yi tsanani nakan ji a raina anya babu k'amshin gaskiya akan abinda ake fadi akanta. Tun farkon neman auranta Sahura ta gaya mini har nake kwa'barta kan tabbatar da abinda baka da sheda a kansa. Na sanya hannu na d'an share guntun hawayen da ya sauka saman kumatuna sun gama karya mini zuciya yaran yayin da tausayinsu ya zauna a zuciyata me

ya fi wannan takaici ace ana binciken sirrin uwarka bayan ta rasu a gano wani abu na takaici wanda ta aikata.
Ban ankara ba kawai na ganta a kusa dani gwiwa a kasa ta kamo hannuna tana fad'in." Anti Amina don Allah ku rufa mana asiri don Allah anti Amina."
Na ri'ke hannunta har na ji yana karkarwa na gane akan abinda take yi wa kuka da tashin hankali kada maganar nan ta fita mutane su gazgata zarginsu.
Sosai na ri'ke ta ina fad'in." Ki kwantar da hankalinki Nusaiba, yadda Ubangijin da ya hallice ta ya rufa mata asiri a lokacin da take raye ya amince da jama'a su ambaci alherinta da kyakykyawan fata har ta rasu to ban ga dalilin da zai sanya don ganin wani sirrinta da ya kasance tsakaninta da Allah ya sanya ni fad'i a gari ba. Na yi miki alkawari kan cewa ni dai babu wanda zai ji haka daga b'angarena, muna ro'kon Allah Ya yafe mata, mu kuma rayuwarmu ta yi kyau a duniya da lahira ."
Ta dinga godiya cikin rawar murya da tashin hankali.
Na ji maganar Salim yana fad'in." Wannan takardun gidan da ta saya ne a kano da filaye uku sai na shagunanta biyu dai na san haya ta kar'ba amma watannin baya kafin ta kwanta ciwo ta ce mini sun gama magana tana so ta biya kudin duka su zama mallakinta."
Ya ce." To tunda ka ga baka ga shedar mallaka ba a cikin wannan takardun da suke hannunka wata'kila ba ta biya su ba, amma dai ka bincika mana wanda suka bata hayar wajan mu ji daga gare su kafin nan sai a had'a kan komai a zauna domin sauke mata nauyi."
Ya amsa a sanyaye yana had'a kan takardun ya mik'a masa ya kar'ba ya mayar cikin dirowar da kudin da sarkokin. Sauran biyun da suka zama na karshen fitowa kama bai mayar da su ba. Tsabar fargaba da tashin hankali a duk lokacin da na dubi mutum-mutimin da ya sha d'auri tamau sai gabana ya fad'i lallai bokan da ya sassa'ka suffofinsu ba 'karamin hatsabibi ba ne. Fuskar Baba sak da yanayin jikin itama suffarta sak rai ne kawai babu a tare da su amma an had'e su waje daya an nannad'e da likkafani da jan zare sai da na k'ura ido ma tukkuna na hangi da wasu 'yan mici-micin layu sun saje da jan zaren ne shiyasa ban gansu ba ga wasu manyan mukullai an had'a an kulle.
Ina can cikin tunani na ji maganarta tana fad'in." Anti mun tafi."
Da sauri na daga kaina ina fad'in." Ki gaishe mini da yaran Nusaiba."
Ta amsa da in sha Allahu kafin su fita da sanyin jiki.
D'akin ya kasance shiru bayan fitarsa.
Ya juyo yana kallona muka zubawa juna ido na dan wani lokaci. Ji na yi zuciyata ta tsinke haka kawai sai na ji ina tausayinsa wace irin masifa ce wannan ni Amina matar nan ashe d'aure mutumin nan ta yi sai ta yi aikin akan ga'ba dama aka ce asiri yana tasiri sosai mussaman idan ya tarar da hali.
Ya d'auki abin zai kwance da sauri na ce." Ka ajiye kada ka ta'ba"
Ya kuwa ajiye da sauri a tsorace yana kallona.
Na ji hawaye sun zubo mini wannan d'aurin ba k'arami ba ne tunda har ta yi masa wannan boyon ina jin tsoron duk ranar da aka warware d'aurin ya fadi

ya mutu ko kuma ya kwanta jinyyya mai tsanani mafiakasari irin wannan mugun aikin wad'anda suka yi sune suke da makarinsa.
Kuka kawai na dinga yi hankalina ya yi bala'in tashi ainun muna cikin masifa ni da yara Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ya zo ya rirrike ni hankalinsa a tashe yana fad'in." Menene abin kuka Amina na amince Maryam ta cutar da ni ta mini illah a rayuwata amma godiyar da nake yi ga Allah yadda ya zaunar mini dake ba ki bar ni ba. Har kullum idan na daga kaina na dube ki sai na ce alhamdulillahi a zuciyata na kuma yi alfahari da kasantuwarki matsayin matata abokiyar rayuwata. Na gode Amina, Na gode kin so ni kin zauna da ni a lokacin da mata suka guje ni, kin yi mini biyayya bisa abinda ranki ba ya so, kin daraja mahaifiyata kin kyautata mata a yau ina gaya miki bayan mahaifiyata ke ce ta biyu a cikin matan da nake alfahari da su, ina so mu kasance tare anan gidan duniya da kuma na lahira."
Kuka na ya sake tsananta jin irin zantukan da suke fitowa daga bakinsa. Gabana ya cigaba da bugawa tsigar jikina na tashi na sanya duka hannuwana biyu na matse shi sosai a jikina ina fad'in." Rayuwarmu da ni da yara za ta shiga garari idan babu kai a cikinta Maryam ta illata mu muddin warware wannan d'aurin da yake tsakaninku ya haddasa masa maka mummunan ciwo. Ko ba ka gaya mini ba kwanciya ciwon da ka yi a kwanakin baya yana da ala'ka da irin ayyukan da ta yi a kanka a jikina na ji hakan mutuwarta abububuwa suka fara lalacewa.
Ya ki'dime sosai yana d'an jijjigani da rawar murya yake fad'in." Ba abinda zai faru, na yarda Maryam ta yi mini illah Amina amma bata samu nasarar kai ni k'asa ba, ga ni ina raye tare dake ta jefe ni sosai ta ko'ina ta dabaibayi ni da d'aurin baki domin kada na hangi lefinta amma ni jin dadina da bata nemi hanyar da zata illata mini ke ba Amina kamar yadda ta ci laya akan Hauwa Allah Ya d'auki ranta kudirinta bai cika ba. Ba ki da hakkinmu da ni da ita shiyasa bata ma yi tunanin cutar da ke ba. Tsafi gaskiyar mai shi na gazgata hakan ne a kwanakin nan da suka wuce da muka je da wani malaminta ya warware ayyukan da ta sanya shi ya yi aikana wannan shine dalilin da ya sanya ni wannan kwanciyar na dinga bacci da ciwon jiki. Ban zalinceta ba amma ni ta zalince ni ta hanyar d'addaureni ta ko'ina babu gaira babu dalili tare da haddasa mini rikici da husuma ta karkashin kasa a gidana. Tunda har ki ka ga na tashi yanzu bayan warware wancen makarun da ta yi mini to warware wannan ma ba zai zama cutarwa a gare ni ba in sha Allahu."
Na dago ina dubansa tare da cewa." Da bakinka fa ka ce tare ku ka je da malamin da ya yi aikin ya warware da hannunsa. To shi wannan din kana da makarin warware shi, ka dubi abubuwan da suke jikinku kai da ita kuma likkafani ne ya yi muku sansani da kai da ita. Wata'kila ta yi aikin ne akan idan ta riga ka mutuwa duk ranar da aka kwance d'aurin da yake tsakaninku kaima ka bi bayanta, idan hakan ba ta samu ka kwanta ciwo mai tsananin gaske."
Ya yi shiru yana kallona a d'an tsorace! sai ya sake matseni gam a kirjinsa yana kiran sunan Allah tare da sake duban idan gunkin mutumin-mutumin na su yake ajiye.

Muka kasance cikin shiru da zullumi jikinsa ya yi bala'in mutuwa ya yi mini wata matsa tsam kamar yana jin tsoron a k'wace ni.
Minti goma a haka muka wanzu babu magana ya cika ni tare da zuwa ya d'auko wayarsa. Ya zauna yana fad'in." Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Kimanin minti biyar yana waya da Malam Rabi'u kafin su yi sallama ya dube ni yana fad'in." Akwai gaskiya a cikin maganarki Amina. Ba ni da masaniyar akan malamin da ya yi wannan aikin don haka dole zuwa kano ya kama ni can kauyen Bunkure wajan Malam D'aha abokin mahaifina ne in sha Allahu ina da yakinin shi zai warware mini wannan d'aurin kuma babu abinda zai same ni da izinin Allah."
Na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." To ita fa waccan kwalbar mai layu a ciki."
Ya ce." Har da ita za mu je gaban Malam din duk abinda yake da akwai Allah zai bayyana shi."

A daran ranar ban iya rintsawa ba har ya ma fi ni tawakkali a wannan ga'bar hawayen idona kuwa ya kasa tsayuwa domin sai nake ganin kwance wannan tsatstsauran d'aurin da yake tsakaninsu zai kassara masa rayuwa idan bai fadi ya mutu ba to ya yi mutuwar tsaye tunda bata raye a duniya to kowace mace ta yi asara. Abinda na ke ji a raina kenan shine kuma ya hana ni sukuni don daga zarar na tuna irin wahalar da ya sha kwanakin da suka wuce sai hankalina ya sake tashi zuciyata tana ta raya mini cewa wannan likkafanin da yake d'aure a jikinsu ita dashi akwai alamar tambaya a kansa tunda duk inda aka ce an yi wa mutum asiri da likkafani ko an binne a makabarta abu ne mai munin gaske. Tsakanin d'azu da safe da yanzu da muke cikin talatanin dare dana juya na kalle shi zan ji wani bala'in tsoro da tausayi da kaunarsa a cikin zuciyata idan ya mutu ni da yara mun shiga masifa wace rayuwa ce za ta biyo bayan faruwar hakan, me zai faru? Maryam ta so zuciyarta ta cuce ni ta cutar mana da yaranmu.
Na jima a sujjada ina kuka ina ro'kon Allah har sheshshekar kukana ya tashe shi ya kira sunana na juya na dube shi yana fad'in." Me yasa wai kike wannan kukan ne? Na gaya miki ba ni so ni shine kadai yafi damuna ki zo ki kwanta babu abinda zai same ni."
Kasa tashi na yi daga saman daddumar na cigaba da jan hanci ina share hawayen da nake ta ko'karin tsayar da shi amma ya'ki yatsuwa.
Ya sauko ya zo ya zauna gabana har da tankwashe kafa. Na kalleshi baccinsa ma yake yi shi kamar abin bai dame shi ba.
Ya ri'ko hannayena cikin kulawa yana fad'in." Ban san haka kike sona da yawa ba Amina, Maryam ashe k'aryar so take yi mini tunda har za ta iya cutar da ni ta hanyar yi mini mugun k'ulli mai razanarwa.
Ha'kikanin so shine irin wannan wanda ki ke yi mini. Kuma na tabbatar da hakan ba tun yau ba daga wajenki Amina, abu daya za ki yi mini yanzu shine ki ji maganata ki share hawayenki ki tashi mu je mu kwanta."
Ya sanya tafin hannunsa ya goge mini fuska kafin ya ri'ke hannuna na tashi da kansa ya cire mini hijab din wuyana muka nufi gadon yana ri'ke da ni sosai a gefansa....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
□□□☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book complete 2k akan telegram. Wshap Gruop 1k via 0542382124....Binta Umar gtbank.*
*07084653262*

*126*
Kwanciya muka yi a tare a gadon ya d'auki kaina ya d'ora saman kirjinsa sannan ya d'ora hannunsa a jikina a hankali ya ja bargo ya rufe mu gabad'aya. Rufe idona kawai na yi ba da niyyar bacci ba domin kuwa babu shi a idona wanda nake da tabbacin shi din bai sake komawa ba har aka kira sallah.
A tunaninsa bacci nake yi ina ji ya sauke  kaina a hankali ya mike ya nufi toilet na tashi zaune ina kallonsa har ya gama abinda yake yi ya fito. Ya d'an tsaya yana kallona na d'an wani lokaci sai kuma ya girgiza kansa kafin ya kama hanyar fita ba tare da ya yi magana.
Sauka k'asa na yi a d'akina na yi wanka na yi sallah a gurguje na kimtsa jikina don babu yadda za a yi ayi wannan tafiyar babu ni.
Na sake komawa saman na shi sai na same shi har ya yi wanka ya shirya yana zaune gefan gado cikin kaftani  gilas da hularsa a gefe yana waya dai da Rabi'un da suka yi magana jiya yana sanar da shi gasu nan zuwa.
Sai da ya gama tukkuna ya dube ni na zauna gefansa tare da gaishe ya amsa cikin kulawa ya dago fuskata muka kurawa juna ido. Kallon da yake yi mini ya kara karya mini zuciya hawaye suka zubo. Ya fara fadin." Kash! menene haka kuma? ki dubi idanunki sun kumbura Amina ni kam na tsanani wannan kukan wallahi." Ya fad'a cike da yanayi na damuwa da tashin hankali."
Sosai na fashe da kukan da karfin gaske ina fad'in." Ni fa wallahi tare za mu tafi."
Ya ce." Akan wane dalili, ai nima ba kwana zan yi ba kuma in sha Allahu da k'afafuna zan dawo gidana, kada ki yarda da abinda zuciyarki take raya miki Amina tunda har na riga na tsallake na baya to wannan ma zan tsallake in sha Allahu."
Na girgiza kaina ina fad'in." Ban yarda ba kawai dai mu je tare na raka ka hankalina zai fi kwanciya."
Ya ce." To yaran fa?''
Ya fad'a yana goge mini kumatu. Na ce." Su zauna wurin su Mairo ai da mutane a gidan ba za su ci karo da wata matsala ba in sha Allahu tunda dama babu wani sabo mai yawa a tsakaninmu."
Ya girgiza kansa yana cewa." To ai so nake ku saba yanzu ki zauna cikinsu sosai ki kula mini da su hankalina zai fi kwanciya ki zauna a gida na je na dawo Amina irin wannan rigimar taki ce fa ta sanya ban sanar dake na farko ba."
Na ce."  Sai ka jefa zuciyata cikin damuwa ba, menene abin boyewa."
"To in banda abinki ai abin alheri shi ake shela, sharri kuwa ba abin fad'i ba ne."
Ya ri'ke hannuna yana duba zoben azurfan da ya sanya mini a yatsana."
A d'an sanyaye ya ce." Kin amince na je na dawo ko matata?"
Girgiza kaina na yi tare da fad'in." Wallahi ban amince ba tare za mu je gashi ma na shirya."
Ya yi jim na dan wani lokaci kafin ya furta." Tunda dai har kin rantse ba zan karya miki ita ba."
Na sauke ajiyar zuciya Ina fad'in." Na kawo maka abinda za ka ci ko?"

Ya ce." Ke 'din kin ci?"
girgiza kaina na yi. Ya furta." To je ki kawo sai mu yi breakfast din tare."
Na tashi da azama na sauka k'asa ina jin dad'in yadda ya amince tafiyar da ni.
To ba mu isa 'kauyen Bunkure ba sai gefin la'asar tafiyar mota ce K
kuma ta samu k'wararran direba Ade wannan karon tare aka tafi da shi su uku da Amintattun yaransa Sukairaju da D'ahuru.
Ko da nake  cikin a garin kano  kafata bata ta'ba taka garin ba sai a wannan karon. Yadda dama muka shirya shine idan har abin ya zo da sauki mun kammala abinda ya kawo mu  gidan malamin sai mu wuce can gidana  na sharad'a mu kwana idan ya so idan mun gaisa da Hajja zuwa jibi sai mu tafi.
Mun samu tar'ba ta mussaman a gidan Malam D'aha. Na ga kara da karamaci irin na mutanan kauye domin kuwa ina idan da sallar magriba aka cika gabana da kwanukan abinci har daga ma'kota. Mafiakasari towo ne na masara dana dawa sai wata langa da aka kawo mini ita daga baya cike da dambu na tsaki wanda ya ji zogale da gyad'a yana ta k'amshin mangyad'a zuryan da yajin barkono a gefe.
Ya ba ni sha'awa sosai na kuma yi masa cin yaushe gamo na toshe cikina da shi duk tarin yunwar dana nad'a a tsukin nan sai da na rasa yadda zan yi da cikina. A daddafe na yi sallar Isha'i. Ina idarwa wata matashiyar budurwa ta shigo doguwa mai duhun fara ba ta da jiki sosai akwai yarinta a tare da ita ta sake gaishe ni na amsa ina fad'in ta kwashe kwanukan abincin da ta dinga kawo mini gasu nan shida a jere.
Ta tsuguna tana bubbud'awa ta dube ni tana fad'in." Ai d'aya kawai ki ka ci Hajiya."
Na ce.'' Ina zan kai wannan abincin yar uwa wannan ma na gode sosai kuma wallahi ya yi mini dadi 'kwarai da gaske."
Ta yi murmushi ba tace komai ba ta fara had'a kan kwanukan tana fita da su.
Na d'auki wayata dake gefena na duba na ga network dina ya d'auke gabad'aya wata'kila yana da ala'ka da yanayin d'akin da nake ciki tunda na 'kasa ne  kuma a k'asa yake sosai.
Gabad'aya hankalina yana can b'angaran malamin tun zuwanmu da muka shiga tare na gaishe shi na fito ban sake jin wani motsi ba sai ta hayaniyar iyalin gidan da shige da fice da ake ta yi na d'aukar abinci daga almajiran malamin.
Gajiya na yi da zaman d'akin na fito tsakar gidan na samu jama'a a cike da yake mai yalwa ne kwarai matan gidan su hud'u suna can daga gefe suna cin abinci a tare wasu daga cikin yaran kuma sun ci sun gama wasu na cin na su. Kwanuka gasunan birjik a bakin manyan tukwanansu.
'Yar budurwar nan da har yanzu ban san sunanta ba na ji tana fad'in." Bandaki za ki shiga.''
Kafin na ce komai daya daga cikin matan gidan ta ce." Hajara zuba mata ruwa maza a buta Hajiya alwala za ki yi ne?"
Na ce." A  ai na yi sallah na fito na sha iska ne." Yarinyar da aka kira sunanta da Hajara ta d'auko tabarma da sauri ta shimfida mini can gefe na je na

zauna ina yi mata godiya cikin ikon Allah zamana ke da wuya network din duka layukana ya dawo.
Na fara neman number Sahura muka gaisa sosai ta sake yi mini gaisuwa nan nake sanar da ita cewar na shigo garin zan kira ta zo gida ta same ni zuwa gobe.
Muna sallama na nemi number Hajja da ta shiga sai ta katse na kira ya kai sau biyar nan na gane network din yake hawa da sauka wai ina so na gaya mata cewar za mu shigo gobe.
Na dauki kimanin minti talatin da zama a tsakargidan wanda ya yi daidai da lokacin tara na dare da minti biyar.
Daga can b'angaran malamin na ji maganarsa alamun zai fito na sauke ajiyar zuciya a hankali idona a kan hanyar suka fito tare da wannan Rabi'u da yake yawan kiransa a waya wanda shine ya kan gaba wurin tararmu lokacin da muka sauka a garin.

littafin gudun aure na kudi kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Suka fito tare da kuzarinsa ya tsaya cikin kulawa yana yi wa matan gidan sallama na tashi ina gyara mayafina na d'auki jakata can inda suke zaune na nufa ina fad'in." Za mu tafi, na gode sosai da karamaci Allah Ya saka da alheri, na dubi Hajara dake zaune cikin 'yan uwanta na ce." 'Yar uwa sai Wani lokacin ko na gode da kulawa."
Ta washe bakinta tana fad'in." Ku gaida gida Allah Ya tsare hanya."
Na ce." Amin Ya Allah tare da yin gaba ganin ya riga ni fita ina jin matan da yaransu suna ta yi mini fatan alheri.
Ina fita daga can wajen motar da mu ka zo Sukairaju nake hange da D'ahuru sai Rabi'un suna taga-taga kafin na hangi Baban ya yi wata irin fad'uwa irin ta ruf da ciki da kirji.
Ade ya fito daga mota a ki'dime! yayin da gabad'aya suka rufu a kansa duk da yake dare ne amma ai irin na karkara ne da suke da wadatar kwanciyar hankali ba irin cikin gari ba hakan ya sanya mutane fara tsayuwa a wajen.
Ban san inda nake jefa k'afafuna ba kawai dai na tsinci kaina a tsakiyarsu lokacin da suke ko'karin ciccib'arsa. Rabi'u yana fad'in da k'afafunsa ya fito kuna dai kallo magana ma muke yi da shi ya yanke jiki ya fadi."
Jikina ya dinga kyarma na tsuguna ina d'ago kansa yana karyewa ganin haka ya sanya ni ihu! ina Kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! Baba  Baba, na dubi Sukairaju a gigice ina fad'in." Ku d'auke shi mu tafi asibiti."
Rabi'u ya ce." Cikin gidan za mu mayar da shi Hajiya ."
Daga haka suka fara kici-kicin ciccib'arsa Sukairaju ya cire gilashin idonsa da wayoyinsa tare da wallet dinsa ya sanya cikin aljihunsa su biyu shi da D'ahuru suka kama saman shi ta wajen kansa. Rabi'u da Ade suka rirrike k'afafunsa a haka ina kallo suka taitayeshi suka koma dashi cikin gidan suna ta Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un.

Na bi bayansu k'afata na karkarwa shikkenan kuma tunda har kansa ya karye ya mutu.
Kai tsaye d'akin malamin suka nufa da shi gidan ya rud'e sosai da hayaniya duk kowa a tsaye na bi su ina kuka na fitar hankali. Babar yarinyar nan Hajara ta zo ta ri'ke ni ta baya ina cire hannunta tana sake ri'ke ni fadi take yi "Yi hakuri ki yi masa addu'a kin ji, Allah ya ba shi lafiya."
Na dube ta ina cewa." Ya mutu ko?"
Sai ta girgiza kanta cikin ko'karin kwantar mini da hankali ta ce." Bai mutu ba ke waye ya gaya miki."
Hawaye ya sake tsinke mini na ce." Kansa na ga ya karye ko'ina na jikinsa ya shika. Kin ga ai lafiya lau ya fito har muka yi muku sallama ko?''
Ta daga kanta cikin alhini ta ce." E, kwarai kuwa amma hakan ba shi yake nuna cewar bashi da rai ba zai tashi in sha Allahu."
Na ri'ke hannunta tamau ina fad'in.'' Ta cutar da ni, ta cutar da yaranmu ta zalince shi, ya yi mata alheri ta saka masa da sharri. Ta gigita mini rayuwata."
Kawai sai itama ta fara kuka ta rungume ni a jikinta tana cewa." Ki yi hakuri ki samu nutsuwa mu je can wajenmu ki zauna ki nutsu kin ji ko, ki yi wa mijinki addu'a."
Hajja ta fad'o mini a rai. Na sake fashewa da kuka mai gunji!
Ta kama ni sosai muka nufi d'an wajenmu a hankali take ta fad'in." Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un. Na kama ni ma idan ta ajiye na d'auka.
Ta zaunar da ni saman tabarma tana cewa Hajara ta d'auko mata mafici.
Ta kar'ba ta fara fifita mini har yanzu ba ta cika ni ba domin ni kaina nasan ba a hayyacina nake ba gabana duf-duf kawai yake yi mini daga zarar na yun'kura zan tashi sai ta riko ni.
Gabad'aya yaransu da manya sun yi cirko cirko a gaba.
Da wani irin sauti na ce." Wayyo Allah anti Yagana kina ina?" Na silale saman tabarmar na kwanta hawaye suka dinga biyo gefan idona. Na riga fa nasan mutumin nan ya mutu kawai a fito a gaya mini ne ba za a yi ba.
Na riko hannunta ina sake tambayarta a karo na biyu ta girkiza kanta tana cewa." Na gaya miki fa bai mutu ba Hajiya yana da rai in sha Allahu."
Na zuba mata Idona kafin na ce." Wuyansa ya karye ana gane alamun rashin rai a jikin dan adam tana nan fa kada ku yaudare ni."
Ta ri'ke ni da kyau a hannunta sai ta dubi yaran tana fad'in." Ku tafi ku yi alwala kowa ya d'auko al'kur'aninsa a yi karatu.
Jin haka ya sanya ni k'ara gazgata abinda zuciyata take gaya mini me yasa ba su yi karatun tun d'azu ba sai yanzu k'wa:kwalwata ta dinga gaya  mini cewa a gidan mutuwa ne kad'ai ake yin karatun al'kurani.
Jakata na d'auka da take ajiye a gefena na d'auko wayata a karo na shida number Hajja na kira ta yi ringing sau biyu a na ukun ta d'aga. Tana magana na yi shiru hannuna yana ta rawa kiran sunana take yi Amina, Amina,  bakina ya yi nauyin gaske hawaye ya ziraro daga idona cikin 'karamin sauti na ce." Ya mutu Hajja ta kashe mana Babanmu Hajiya Maryam ta cuce ni......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*

[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: *Gudun aure paid book complete 2k k akan telegram normal What'sapp group kuma 1k via 0542382124.... Binta Umar Opey bank*
*127*
Da tsananin damuwa nake jin ta tana kiran sunana na ajiye wayar ba tare da na kashe ba jikina na rawa sosai na 'kunshe bakina da hannu jin yadda wani mahaukacin kuka ke ko'karin kufce mini.
Mahaifiyar Hajara da na ji suna kiranta da Inno ta d'auki wayar tana fad'in. Hajiya halima ce. Daga daya bangaran ita hajjan tana ta fad'in." Ko Baba Sulen ya rasu Amina domin shekaran jiya Kamalu ya ce mini ya je ya duba shi a can asibitin Murtala an kwantar da shi. Amina, Amina kina ji na."
Ta ce." Ni ce Inno uwargidan Malam D'aha nan Bunkure."
Hajja ta ce." Inno me yake faruwa ne, wanene ya rasu ina Amina take?"
Duka ta jero mata wad'an nan tambayoyin.
Cikin sigar kwantar da hankali ta ce." Babu wanda ya rasu Hajiya Halima gigitace dai kawai ta sanya har ta gaya miki haka."
Ta ce." Inno ki gaya mini gaskiya kin san dai ni ba yarinya ba ce?"
Sai ta dabarbarce ta kasa gaya mata komai. Zuciyata ta sake karyewa tabbas bata da abinda za ta fad'a kuma da bakinta take cewa bai mutu ba gashi yanzu an tambayeta ta yi shiru.
Ina jin Hajjan tana ta magana Inno ki gaya mini menene, ki bawa Amina wayar mu yi magana na ji ta a kusa dake tana kuka."
Ta miko mini wayar jikinta a sanyaye. Na kar'ba nasa a kunnena na ji tana fad'in." Yi shiru ki kwantar da hankalinki Amina ki gaya mini abinda yake faruwa kin ji ko, ki gaya mini ko menene ina sauraranki."
Da kyar na daidaita kaina na ce." Muna nan Bunkure ni da Baba amma ban san halin da yake ciki ba yanzu Hajja ki zo don Allah."
Ta ce." Yi shiru zamu zo in sha Allahu, yanzu dare ya yi amma da asuba zamu d'auko hanya dukkan tsanani yana tare da sauki."
Ban iya cewa komai ba sai jan hanci na ji ta kashe wayar sai ni ma na ajiye tawa na matsa jikin bango na takure can 'kasan zuciyata ina ta ambaton Allah akan ya kawo mana d'auki.
Dare ya tsala sosai muna zaune a tsakargidan ni da Inno mu biyu kacal ta yi ta yi da ni na shiga na kwanta na ce mata ta barni ko na kwanta din ba bacci zan yi ba gabad'aya hankalina na sashen malamin shiru ya hana kowa shiga Sukairaju da yan uwansu su Dahuru tunda suka shiga dashi ban sake ganin gilmawarsu a hanyar ba Rabi'u ne ya shiga sau d'aya kafin ya fito ya nufi bangaransa dake cikin gidan bai sake fitowa ba. Muna zaune har aka kira sallar asubahi. Kowa ya fito ya yi alwala yara da manya na yi na shiga d'akin da suka sauke ni a tun farkon zuwanmu gidan na yi sallah ina kuka sosai ina yi wa rayuwarmu addu'a.
Karatun al'kurani tun daga almajiransa na waje da cikin gidan iyaye da yaransu. Na kar'bi al'kur'ani wurin Hajara na bude nima ina karantawa a hankali a hankali na ji zuciyata tana sanyi. Gari ya fara haske Hajja suka shigo gidan ita da Hajiya Saratu da kanin mahaifinsa alh Sa'idu.
jin maganarsu ya sanya na rufe al'kur'anin da sauri na fito tsakargidan.

Inno ta sauke su tare da shimfida musu tabarma  suka zauna yanayinsu ya nuna tsantsar tashin hankali a haka suka dinga gaisawa da jama'a.
Ba su wani jima da zama ba. Rabi'u ya fito daga wurinsa suka gaisa a gurguje ya nufi sashen malamin minti biyar a tsakani ya fito tare da fad'in." Hajja Malam yana magana."
Kusan a tare muka tashi gabad'aya ya shige mana gaba kowanne mu zuciyarsa na dokawa.
Yana zaune saman buzu da al'kur'ani warshu mai falle-falle a hannunsa d'akin tsaf Y
yana ta k'amshin turaran wuta. Can muka hange shi kan wata katifa madaidaiciya da shimfidar bargo a samanta. Yana kwance sambal sun cire masa rigar jikinsa daga shi sai singileti da dogon wandon rigar da suka cire hannayensa nade a k'irji ido a rufe.
Kafafuna suka fara kyarma Hajja kuwa kuka ta sanya tana fad'in." Me ya faru Malam ma'kiyane suka jefe shi ko, Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ta nufe shi tana kuka sosai ta tsaya a kansa tana fad'in." Ni kuwa me ka yi wa jama'a ne Tajo daidai gwargwado kana alheri da kyauta da yawa wasu na ta ganin wautarka akan dukiyar da Allah Ya baka. Ka yi kyautar hajji ka yi ta umara, ka yi kyautar kud'i ka yi ta gida da mota da jari, duk hakan bai yi musu ba sai sun kwantar mini da kai."
Shiru d'akin ya yi tana kuka da sambatu Hajiya Saratu na kusa da ni tana goge hawaye ta ma kasa zuwa inda yake kwance. Gabad'aya ta gigice sai kuka take yi na kasan zucciya.
Ni kam idona bushewa ya yi k'amas ban yi mamakin hakan ba wata'kila hawayen idona ne ya 'kare sai dai wani kutittiran abu da nake jin sa ya tokare mini a wuya. Da na d'aga kaina na dubi wurin da yake kwance sai gabana ya yanke ya fadi.
Alhaji Sa'idu ya tashi a hankali ya je ya kamo hannun Hajja ya zaunar da ita a gaban malamin wanda tunda take koke-koken bai ce komai ba.
A nutse ya had'a al'kur'anin da yake hannunsa ya mayar da shi ma'adanarsa ya kalli Hajja da har yanzu ta kasa nutsuwa ya ce." Hajiya Halima kukan ya isa haka, mu godewa Allah da ya  takaita lamarin kuma aka samu hanyar warware shi cikin sau'ki.

Littafin nan na kudi ne yar uwa kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Kamar yadda ki ka sani dai ni malamin zaure ne mai almajiran mai kuma hidima da al'kur'ani. Na ji dad'i sosai da Allah ya tsawaita mini nisan kwana wannan al'amarin ya kasance ya kuma ba ni iko da damar warware shi. Ba ni cutarwa ta hanyar sanin da Ubangiji ya ba ni kamar yadda wasu malaman suka d'auki wannan hanyar ta zalinci domin neman abinci da cutar da hallitar Allah.
Hakika a wani zuwa da Alhaji Tajo ya yi gare ni wattanin baya na karanci akwai rikici da makaru a tattare da shi. Wannan dalilin ne ya sanya ni gaya

masa cewar ya dage da addu'a akan shi da kuma yaransa idan ban manta ba na tambaye shi iyali da adadin yaransa ya sanar da ni. Na bashi adduoi sosai na kuma yi masa da kaina domin samun mafita da warware wa.
jiya suka zo nan da matarsa ya yi mini bayanin dukkanin abinda ya faru bayan rasuwar matarsa Maryam wadda itace musabbabin kwantar da shi tunda aikin da ta sanya aka yi akansa ni kaina ya tsorata ni ba don komai ba sai don ganin irin d'aurin da aka yi masa bayan lokacin da Ubangiji ya d'iba masa bai cika ba.
Na jima ina aikin warware asiri iri iri wannan ya ba ni mamaki ya kuma tsoratar da ni k'warai da gaske, kuma an cire tsoron Allah wajen aikata shi.
Ya yi shiru yana duban inda yake kwance tare da girgiza kansa tabbacin da gaske abin ya bashi tsoro da mamaki kamar yadda ya fad'a..
Hajja ta ce.'' Ni ai a zatona abokan kasuwanci ne ko wasu da ba sa kaunarsa suka jefe shi tunda kasan yadda duniyar take."
Ya girgiza kansa yana cewa iyalinsa ce Hajiya halima kin san ku mata wani lokacin da son kai kuke da kuma mugunta. Ba dai a tara sani da Allah wata'kila ta ji a jikinta za ta riga shi mutuwa ne sai ta yanke shawarar yi masa d'aurin rai da ajali idan ta rasu a cikin biyu ko ya bi bayanta ko kuma ya kwanta kamar dai yadda yake a haka yana numfashi amma bai san a duniya yake ko a lahira ba."
Shiru ya ratsa kafin ya cigaba da cewa jiya na kwanta bacci bayan na yi sallar istahara akan lamarin domin kara tabbatarwa Ubangiji Allah Ya nuna mini ita ko ba ita ce 'yar fara mai karamin jiki ba da doguwar fuska?"
Hajiya Saratu da sauri ta ce." K'warai itace malam suffarta kenan."
Ya gyad'a kansa cikin jajantawa yana fad'in." Rahama sai ta Allah a wajen da take domin irin shirkar da take yi Allah Ya la'ancesu. Ba za mu yanke hukunci kai tsaye a kanta ba amma tunda har son zuciya da mugunta ya sanya ta kafurta kanta ta iya yadda da juya zancen Allah wurin neman biyan buk'atarta tabbas alkawarin Allah baya ta shi."
Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Na warware duk d'aurin da ta yi a kansa da yaransa zai tashi da izinin mai buwaya. A yadda ta so shine ko ya tashin ya zama mutumin-mutumin kamar gunki tunda da ayar nan ta (Summunbukkum!) aka yi aiki akansa bayan ita suka had'a (Makisinafiyiabada) ayoyi ne masu zafi wurin dakusar da duk wani karsashin dan adam idan aka juya su ta gefan zalinci.
Ita kuma wannan kwalbar ya fad'a yana nuna musu ita ya cigaba da cewa." Kowacce laya akwai sunan mutum guda a ciki. Amina Hauwa Kamalu Yusuf Khalil Hassana Usaina da kuma Minal. Mallaka ce aka yi akan wad'annan sunayen da na zayyano da kuma jefa soyayya a zuk'atansu.
Hajja na kuka tace fad'in." To me ya yi mata ni Halimatu na ga da iyalinsa ta same shi. Tsananin abotar da take tsakaninsa da Alhaji Amadu ya sanya da ya rasu ya aureta ni ma na bashi goyon bayan yin hakan tunda ya gaya mini a rubuce aminin nasa ya bar masa wasiyyar yin hakan. Me ya yi mata da zafi irin haka da za ta yi masa wannan mugun asirin."
Ya ce." Son shi take ainun kuma macace mai zafin kishi abinda na fahimta kenan."

Hajiya Saratu ta ce." Mun gode sosai Malam Ubangiji Allah saka da alheri, yanzu ya yanayin jikin nasa." Ta fad'a tana kallon wajen da yake.
Ya ce." A nan za ku bar mini shi daga nan zuwa sati guda zai warware in sha Allahu rabbi zai tashi ya cigaba da gudanar da al'amuransa."
Alhaji Sa'idu ya ce." Malam abin nan ya jefe ni a rud'ani ba kad'an ba. Ashe akwai irin wad'annan matan marasa Imani da tsoron Allah wallahi idan ana fad'a ba ni gazgatawa."
Ya ce." Akwai su da yawa muna ta fama da su. Ita wannan nata akwai razani k'warai domin tana iya bada jinin adam akan biyan buk'atarta tana aiki da ba'kar iska kuma suna iya neman jinin kowacce irin hallita. Kuma suna nan da yawa. Abinda dai na fahimta ga sha'aninta shine macace mai zafin kishi da mugunta. Kamar yadda na gaya muku da farko ni ba na bugun 'kasa akan neman sanin abinda Allah rufe bai bayyana ba. Istahara irin wadda Annabi ya koyar ita nake a duk dare kan wata mas'ala da aka kawo ta gabana idan na kwanta bacci Allah Ya akan nuna mini abinda yake faruwa. Iya fahimtata soyayyar da take masa ne ya sanya ta aikata masa haka saboda kishin ko bayan ranta kada wata mace ta more shi wannan shine
abinda ya halakar da ita har ta k'etare iyakar Ubangiji."
Hajja na girgiza kai tana fad'in." Kin yi kyawun dan maciji Maryam kin ci amanar mijinki, kin ci amanarmu da muka so ki muka kaunace ki, kuma duk inda muka zauna muke fad'in alherinki. Kin zalinci Tajo da iyalinsa kin mutu ba ki nemi gafara ba zahiri ba mu yafe miki ba maryam "
Tasa gefan mayafi ta goge hawayenta cikin damuwa.
Ya ce." Matarsa ta zauna nan har tashon kwanakin dana d'auka in sha Allahu komai zai wuce kamar ba a yi ba."
Hajiya Saratu ta ce." To shikkenan Malam yadda ka ce haka za a yi Allah Ya saka da alheri amma za mu dinga zagayowa muna duba shi ko?"
Ya ce." Hakan yana da kyau in sha Allahu."
Muka fito daga d'akin a tare da d'an sasaauci ba kamar lokacin da muka shiga ba cikin tsananin tashin hankali.
Hajja ta fara rigima wai itama sai ta zauna. Da kyar da jibin goshi Alh Sa'idu suka rarrasheta kan cewa ta yi hakuri su tafi idan ya so duk bayan kwanaki biyu sai su dinga zuwa.
Sai da suka yi sallar Azhar suka ci abincin suka yi shirin tafiya lokacin malamin ya yi b'aki ba su samu damar yin sallama da shi ba.
Tunda ba kasafai ake shiga wurinsa ba sai ya yi izini.
Da magriba yarinyar nan Hajara ta sake kawo mini dambu cikin langa tana fad'in.Matar yayansu ce ta ce a kawo mini tunda na jiya ya yi mini dadi.
Godiya na yi mata sosai na daure na ci ba don yana yi mini dadi irin na jiya ba sai don korar yunwa. Ba ni son na kwanta ban sake ganinsa ba.
Na fito tsakargidan suna zaune iyayen da yaran. Ban san ina su Sukairaju suke ba nasan dai tunda gidan karamci ne za a kula da su. Ina so ya je ya d'an yi mini sayayyar cikin kasuwa ko dogwayen riguna ne na yi na yi na kira Sahura a waya ta'ki shiga ina so na ce mata ta je can gidana ina da kaya ta debo mini sai ta kawo mini ba a samu network mai karfi a gidan sai an fita waje a tsakargidan kuma idan ya hau sai ya sauka haka yake yi.

Ina tsaye da waya a hannu Malam Rabi'u ya zo yana gaishe ni na amsa cikin dan jin nauyi domin yanayin yadda yake risina mini na sanya ni jin kuny. Ya tambaye ni ko ina da buk'atar eani na ce masa ina son na yi magana da Sukairaju.
Tare muka nufi wajan da aka sauke su. Ya fito ganina a tsaye ya risina na ce." Garin nan babu network mai karfi kasan gidan Sahura ko?''
Ya ce." E, na sani."
Na d'an yi shiru ina kallonsa gabad'aya shima baya nutsuwarsa botiran rigarsa duk sun zube idonsa ya yi ja da alamun bai samu bacci ba..
Na ce." Gidana na can kuntau can ta koma da zama."
Ya gyad'a kansa yana kallona na ce." Ku je tare da ita can gidana na sharad'a za ta debo mini kaya sai ka kawo mini akwai mukkuli a hannunta."
Ya ce." In sha Allahu zan yi wanka yanzu na tafi amma ya jikin oga, mun tambayi Malam Rabi'u ya ce mana da sau'ki ."
Na ce." Da sauki alhamdulillahi amma ku taya shi da addu'a domin ita ya fi buk'ata a yanzu."
Ya ce." In sha Allahu Hajiya amma a wane hali yake ciki yanzu ya tashi ne muna ta so mu shiga mu duba shi ba a ba mu dama ba ."
Na ce." Yana dai kwance har yanzu yadda kuka d'auke shi Sukairaju."
Sai ya yi shiru yana kallona cikin damuwa. Na juya ina fad'in.'' idan ka je ka dawo sai ka sanar da ni."
Na samu Rabi'u a soro a tsaye na ce." Ko za a yi mini iso wurin Malam zan shiga."
Da sauri ya ce. Eh amma yana d'an wani aiki yanzu zuwa an jima idan ya kammala zan sanar da shi sai ki shiga ko"
Na ce." To shikkenan na gode sosai. Ciki na shige gabad'aya jikina a sab'ule har in dai Hajiya Maryam ta samu nasarar nakasta mutumin nan ya tashi da wata tawaya ta cuci mutane da yawa wad'anda suka dogara da Allah suka kuma dogara da shi, halin da Sukairaju ya shiga yanzu abin jajantawa ne da tausayawa, to balle kuma yaransa da wad'anda suke makusantansa....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu.

Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book complete 2k akan telegram normal What'sapp group kuma 1k via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*128*
Haka na yi ta zaman jiran ganin Malam Rabi'u ya yi mini izinin shiga d'akin malamin shiru har dare ya yi nisa ban ji daga gare shi ba hakan nan na ha'kura na kwanta a wannan daran ma bacci sai dai b'arawo domin da ya d'auke ni na 'yan mintina zan bud'e ido har dai asubahi ta yi motsin iyalin gidan ya sanya ni tashi na fito da buta cike da ruwa wadda Hajara jiya ta ajiye mini kafin ta je ta kwanta.
Na jima saman abin sallah ina jan carbi bacci ya fara shammatata tunda dama shi ba a cin bashinsa. Na ji maganarsa yarinyar tana fad'in." Ina kwana."
Na bude idona da sauri tare da shi zaune ashe har na kai ga kwanciya kan daddumar ta ajiye mini dogon kofi na kunu da silbar k'osai a gabana ta juya ta fita minti biyar a tsakani ta dawo da wata langa ta ajiye mini da ruwan pure water guda biyu.
Na bude langar dumamen towo ne na masara miyar kuka tana ta k'amshin daddawa da zafinsà nan da nan yawuna ya tsinke na mike na fita.

Yaran gidan da alama sun shiga makaranta domin shiru babu hayaniya kamar koyaushe. Inno na bakin tukunya da kwanuka a gabanta ta juyo tana kallona sai ta saki fuskarta tana fad'in." Hajiya kin fito.
Na daure sosai ganin yadda matar ke ko'karin ganin lallai sai ta faranta mini da kwantar mini da hankali na ce." Eh ina kwana ya hidima na gode sosai Allah Ya saka da alheri.".
Ta amsa cikin dadi tana fadin." Ai na ce Hajara ta kawo miki dumame nasan zai yi miki dadi."
Na ce." Sosai ma kuwa wallahi Allah Ya saka da alheri."
Ta amsa da Amin ya rabbi." Bakina na wanke na koma d'akin zuciyata cike da zullumi haka na ci towon nasha ruwa d'aya na fito tsakargidan shiru matan gidan na d'akunansu.
Can bakin 'kofar fita na nufa na lura wajen akwai network sosai na kira Sahura muka gaisa na ce." Sukairaju ya zo jiya ne?" Ta ce." A a sai yanzu dai ya zo kin ga ina shiryawa wai me yake faruwa ne ya ce mini Yallabai ne bashi da lafiya kuna kauyen Bunkure."
Na ce." Sahura abubuwa da yawa sun faru masu muni ba zan iya ba ki labari a waya ba amma ina cikin tashin hankali mai tsanani"
Ta ce." Idan babu damuwa zan iya biyo Sukairaju ko Amina wallahi hankalina ya tashi ban san a wane hali ki ke ciki ba." Cikin rauni take maganar. Na ji zuciyata ta yi nauyi lallai Sahura masoyiyace ta hakika duk lokacin da na shiga matsanancin hali takan rasa sukuni tun muna 'yan mata haka muke idan daya ya shiga wani yanayi duk sai mu rasa sukuni."
Na daure na ce." Me zai hana ki biyo shi amma bai zama lallai ki samu ganin Yallaban ba tunda ni ma sau daya na ganshi malamin baya bari."
A sanyaye ta furta." Zan dai biyo shi Amina domin ganin halin da ki ke ciki idan kuma ina da sa'a sai  Allah yasa a bar ni na shiga na duba shi din."
Na ce." Shikkenan duk abinda ki ka san zan buk'ata ki kawo mini Sahura zama ya kama ni dole."
Ta ce." In sha Allahu."
Na kira layin Anti Yagana cikin sa'a ta shiga na sauke ajiyar zuciya ina jiran ta daga na ji maganarta tana kiran sunana na amsa a sanyaye.
Ta ce." Ya aka yi Amina ya kuke ya yaran fatan kowa lafiya, ki yi hakuri sosai domin ke nauyi ya hau a yanzu ki yi kokarin ganin kin ri'ke yaran nan na Maryam tsakani da Allah domin ki rabauta da lada."
Na ce." In sha Allahu anti Yagana amma akwai matsala fa."
Ta ce." Menene kuma?"
Shiru na yi domin ban ma san ta yadda za a yi na fara yi mata bayani ba.
Ta sake maimaita tambayarta murya na rawa na furta." Maigidan ne ba shi da lafiya anti Yagana ina nan kano wani gari Bunkure ana yi masa magani."
A dan tsorace ta furta." mai ya same shi Amina amma tun yaushe me yasa ba ki gaya mini ba?"
Na ce." Anti Yagana duk yadda za a yi na yi miki bayani ba za ki fahimta sosai ba tunda a waya ne, abinda zan iya ce miki anan shine matarsa ce da ta rasu ta yi masa asirin rai da rayuwa yanzu haka yana kwance sai dai a kwantar a tayar bai ma san a ina yake ba."

Sosai ta ki'dime tana fad'in." Maryam d'in Amina wane irin asiri ne wannan an ya kuwa babu sanya hannun magauta kin san fa ba zai rasa makiya na fili da boye ba don Allah ku daina amincewa da jita jita akan matar nan."
Murmushin takaici na yi tare da fad'in." Ba za ki gane ba ne ai anti Yagana kawai idan da hali ki zo sai ki ji komai ba sharri ake yi mata ba wallahi da gaske ne ga zahiri ya bayyana bayan rasuwarta."
A sanyaye ta ce." Zan zo in sha Allahu tunda jikin baba Sule babu dadi an ce yana kwance a asibiti sai na duba shi."
Na ce." Haka na ji a wajen Hajja ban sani ba wallahi yaushe za ki zo."
Ta ce." In sha Allahu cikin satin nan, zan dai kira ki."
Na ce." To shikkenan anti Yagana"
Sallama muka yi cike da yanayi na damuwa domin abin ya doke ta itama kwarai da gaske.
Wajajen daya da minti goma Sahura ta shigo ina d'aki a kwance na yi muryarta suna gaisawa da matan gida yara suna ta gaisheta sannan suka nuna mata d'akin da nake.
Ina kwance ban motsa ba ta shigo da k'aramar akwati a hannunta..
Na tashi zaune ina kallonta ta zo ta zauna kusa da ni hankalinta gabad'aya a kaina sai na ga ruwan hawaye ya ciko idonta ta ce." Amina ke ma jinyyar ki ka yi ne?"
A tak'aice na ce." Me ki ka gani ne?"
"Kin rame sosai wallahi kin yi wani iri?"
Ban ce komai ba na zuba mata ido ina kallonta ta goge hawayen da ya d'an zubo ta riko hannuna a sanyaye tana fad'in." Menene yake faruwa don Allah ina Yallabai din Amina na ji tsoron ganinki a hargitse cikin k'unci da damuwa."
Na yi ta ko'karin ganin na hana hawayen da yake dannowa zuba amma sai da ya fito ban goge ba na ce." Sahura ashe maganar nan da ki ka gaya mini farkon jin labarin auran Hajiya Maryam a wurin aikinku da gaske ne, ta asirce mini miji ta bi yaranmu daya bayan d'aya ta asirce ko na ce ta tsaface domin haka malamin ya fad'a tsafi take yi."

littafin nan na kudi ne Hajiya kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ta gyad'a kanta cikin al'ajabi tana kallona sannu a hankali na shiga warware mata tun daga farkon lamarin har zuwa yanzu da za a kira da fad'an k'arshe tunda komai ya bayyana.
Ta jima shiru cikin tsananin tashin hankali da mamaki kafin ta ce." Anya matar nan mutum ce Amina wane irin zalinci ne wannan. Mutum ta aure shi da iyalinsa da yaransa saboda tsabar mugunta  da son zuciya. Wallahi tunda labari ya fasu a wurin aiki nake ta jin ana magana akanta har na gaza ha'kuri na gaya miki amma kin san abinda hana a gazgata gaskiya ne ayyukan da take yi na alheri da suke a bayyane shine dalili da ya sanya da yawa wasu ba su yarda da wancan zargin ba. Wai akan namiji Amina ki ga mace ta yarda ta

mutu a matsayin 'yar wuta domin dai Hajiya Maryam babu abinda zai hana Ubangiji bai hukuntata ba idan an yi duba da irin ayyukan zalincin da ta gudanar a lokacin da take raye."
Na ce." K'warai kuwa Sahura a raina nake jin idan har mutumin nan bai tashi da lafiyarsa kamar da ba to har na koma ga mahallicina ba zan yafe mata ba zan ta yi mata addu'a har karshen numfashina.
Ta ce." Don kin yi hakan ba lefi ba ne Amina ta cuceku wallahi kuma ta cuce mu domin duka hanyar abincinmu tana ga Allah tana hannunsa babu abinda za mu yi masa sai dai addu'a Allah ya saka masa."
Hajara ta shigo da tire na silba jera da kwanukan abinci ta ajiye a gabanmu ta fita ta sake shigowa da ruwan pure water a leda ta dube ni tana fad'in." Hajiya ruwan da ki ka ce a dora miki ya yi har na kai miki bandaki."
Da kulawa sosai na ce to na gode kwarai Hajara Allah Ya yi miki albarka."
Ta juya ta fita da sauri. Na dubi Sahura ina fad'in." Akwai brush a kayan ko?" Da sauri ta ce." E a kwai na tsaya na sayo."
Ta fito mini dashi tare da matsa mini abin goge bakin da sabon soso da sabulu na kar'ba na fita
Sai da na fara wanke bakina tukkuna na shiga bandakin tsaf da shi cikin tsafta duk da na gargajiya ne ba zaka taba ce wa na had'aka ba ne suna da tsabta da kula sosai kuma sun horar da yaransu aiki da tarbiya."
Sai bayan la'asar tukkuna Sahura ta yi shirin tafiya ba tare da ta samun ganin Yallabai din ba Sukairajun dai shine ya mayar da ita bai dawo ba sai bayan ishai.
To a washe garin ranar da Sahura ta zo su Hajja suka sake zuwa tun safe haka muka yini tare da su a wannan karon ma ba su samu damar ganinsa ba haka suka hanya suka tafi cike da matsanaciyar damuwa.
Kwanaki hud'u yana kwance shi ba mai rai ba shi ba matacce ba numfashi ne kadai ke nuna tabbacin da rai a gangar jikinsa na shiga na gan shi da safe amma ban iya zaman minti biyar a d'akin ba na fito 'kafafuna suna rawa a ranar kuwa yini na yi a kwance abinci bai samu shiga ba sai dai zubar hawaye da k'uncin zucci. Idan har mutuwarsa za ta sassauta masa wannan mawuyancin halin Allah Ya gaggauta yanke hukunci a kansa. Idan na rintse idona sai na dinga ganin kamar a mafarki na dinga tariyo irin rayuwar da muka dinga gudanarwa ni da shi daga lokacin da muka hadu har kaddarar aure ta ratsa tsakaninmu da irin rigingimun da muka dinga yi kamar za mu halaka juna da fushinsa da gabarsa da kuma tausayi da alherinsa sai uwa uba tsananin soyayyar da yake nuna mini.
Na dubi zoben azurfan da ya sanya mini a yatsa ina tuna lokacin da ya sanya mini shine sai da ya gama tsokanata da wasa da dariya abu ne mai muhimmanci a gare shi dalili zoben mafiakasari an fi samunsa a hannun shahararrun Malamai yan siyasa masu kudi ko masu mulki azurfa ce ta mussaman a wajensa amma tsananin yadda yake k'aunata ya kama yatsana ya sanya mini shi.
Na sa hannu na goge hawayen da suka zubo mini tare da jan hanci Ina tuna yadda muka dinga da k'ullatar juna rikicin da ya kaimu har gaban baban saude ashe akwai abinda Allah ya shirya shiyasa a duk lokacin da na samu

ciki yake gaya mini yana so ko da za su kasance masu nakasu. Maryam ta yi wa rayuwata illah Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! Nasa hannu tare da rufe bakina jin sautin kukan da nake yi na ko'karin fita.
Ina cikin wannan yanayi na 'kunci da neman taimakon Allah na ji muryar Malam Rabi'u ban motsa ba amma hankalina na wajen domin in bayan malamin shine mutum na biyu da yake dawainiya da Yallabai din mahaifiyarsa Inno shi take tambaya halin da ake ciki.
Na ji shi cike da annashuwa da kuma murna yana fad'in." Wallahi yanzu nan ya motsa Inno ya kuma fara da sunan Allah, ina alfahari da kasancewar Malam a matsayin mahaifina Ubangiji yakan taimake shi akan duk abinda ya sanya a gaba. Wallahi ban ta'ba tunanin Alhaji Tajuden zai tashi da nutsuwa da hayyacinsa ba Inno idan an yi duba da yanayin yadda muka shigo dashi a lokacin da ya fadi, cikin ikon Allah Ya yi magana har ya kira sunana a cikin hayyacinsa ya kuma sheda cewa a gidan Malam yake.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran

gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book 2k complete on telegram what'sapp Gruop 1k. via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*129*
Da wani irin yanayi na godiyar Allah na tashi zaune na dubi gabas sujjudur-shukur ta godiya ga Allah na yi ina kara jadadda tasbihi a gare shi lallai Ubangiji mai ji ne da gani kuma maji ro'kon bayinsa ne.
Na dago da tarin tahamidi a zuciyata inno ta leko fuskarta a washe tana fad'in . Hajiya Amina ko bacci ki ke yi ne alhamdulillahi maigidanki ya tashi yanzu nan wannan yaron yake gaya mini.
Jin yadda ta kira shi da wannan yaron ya sanya ni gane cewar d'anta ne na fari.
Ina murmushin da ni kaina ban san kalarsa ba dole sai mai kallona ne zai gane wane iri ne na ce." Na ji lokacin da yake yi miki bayani, Ubangiji mun gode maka, Inno Allah Ya karawa malam lafiya rabbi ya saka da alheri."
Ta amsa da "Amin Ya Allah yanzu kam ai sai ki ci abinci ki dan fito cikin jama'a ko?"
Na ce." In sha Allahu rabbi a kawo mini abincin."
Ta saki laluban d'akin da sauri na ji muryarta tana kiran sunan Hajara. Na sake daga hannuna ina fad'in." Allah Ina sake godiya a gare ka, na gode Allah ka karawa Annabi daraja."
Hajara ta ajiye kwano biyu na abinci da ruwa. Na bude na farko alala ne da manja da yaji da maggi d'unkule a gefe d'aya kwanon kuma shinkafa da wake ne yana ta k'amshin mangyada.
Alalan ne ya ba ni sha'awa tunda harkar manja da yaji ne bakina kuma dama babu wani d'and'ano.
Shida ne manya na ci hud'u cikina ya cika sosai na sha ruwa na fito tsakargidan. Yaran sun shiga makarantar dare sai iyayen suna ta hira akwai mutunta juna a tsakaninsu duk kwanakin da na yi a gidan har yanzu na kasa tantacce 'yayan kowacce dalili yaran kansu a hade yake kamar iyayen kuma suna mu'amularsu a kowane d'aki.
Cikinsu na zauna muna hira daya daga cikinsu da na ji suna kiranta da Uwa ta fara tsokanata tana fad'in." Kuka yake 'kare Hajiya."
Dariya kawai na yi na sunkuyar da kaina kasa ina jin nauyi tare da tuna abinda ya faru a tsakanin kwanakin..

Muna zaune Rabi'u ya shigo da wayoyinsa Yallabai din a hannunsa. Ganina cikin iyayensa ya sanya shi washe baki ya tsaya da kulawa muka gaisa kafin ya ce." Gashi har ya yi wanka Malam ya bashi daya daga cikin tufafinsa ya sanya ya ci abinci ya kuma buk'aci wayoyinsa ."
Na ce." Ma sha Allah Ubangiji Allah Ya kara bashi lafiya."  Ya nufi wurin malamin a gaggauce na kasa jurewa a hankali na ce." Za a  iya sanar da mahaifiyarsa ko?"
Ya ce." K'warai kuwa Hajiya."
Na tashi na je na d'auko wayata na dawo na zauna. Cikin ikon Allah na samu network na kira layin Hajja ta katse ba a daga ba. Kira na biyu na ji muryar Kamalu ya gaishe ni na amsa ina tambayarsa Hajja ya ce." Tana d'aki a kwance tun safe da suka dawo daga asibiti.
Da sauri na ce." Wanene lafiya?"
"Itace yau ta tashi da jiri shine Hajiya Saratu ta zo ta d'auketa suka je asibitin Malam Aminu likitanta ya dubata amma dai alhamdulillahi tunda yadda ta fita da kafarta haka ta dawo da k'afafunta ta kuma ta ci abinci tasha magani shine bacci ya kwasheta."

littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Ajiyar zuciya na sauke da damuwa na ce." To Allah ya sawakke kada ka tasheta yanzu da safe dai kace mata na kira ta.''
Ya ce." To Mama amma ya jikin Baba?''
Na ce." Jiki alhamdulillahi Kamalu yanzu ma kiran da na yi mata kenan domin na gaya mata cewa ya tashi har ya ci abinci ana hira dashi."
Ya dinga fad'in." Alhamdulillahi Ubangiji Allah mun gode maka."
Na ce." Da safe zan kira in sha Allahu" Daga haka sai na datse kiran na nemi Hajiya Saratu bugun farko ta shiga ta daga na ji muryarta cikin tashin hankali tana fad'in." Amina Allah dai yasa lafiya."
A tsanake na ce." Lafiya lau Mamana na kira ne domin na yi miki albashiri."
Ina jin lokacin da ta saki ajiyar zuciya a kagauce ta furta." Ya tashi ne?"
Na ce." E, wallahi cikin nutsuwa kuma yadda mai dawainiya dashi yake fadi har ya yi wanka ya ci abinci ya kuma buk'aci wayoyinsa."
Ta dinga godiya ga Allah ina jinta muryarta har tana rawa take fad'in." Amina wallahi da na ga kiranki da farko sai da gabana ya yanke ya fadi haka kawai sai zuciyata take raya mini za ki ce mini Tajo ya rasu. Yau tun safe na kai Hajja asibiti saboda ta kasa nutsuwa bata bacci ba ta cin abinci hakan ya haddasa mata jiri da ciwon kai kuma kin san tana da hawan jini  fadi take yi wai ta san ya rasu b'oye mata ake yi."
Na ce." Na kira Kamalu yanzu ai yake yi mini bayani na ce to bari na sanar dake tunda yace bacci take yi."
Ta furta." Ai yanzu zan sake komawa gidan in sha Allahu. Amina mun gode sosai lallai mata suna suka tare a gidan Tajo ina yi masa murna ya yi dace da mace tagari mai tausayi da kuma soyayya ta domin Allah. Abinda Maryam ta

yi mana kuma mun barta da hasken rana fad'uwarta Ubangiji shi zai yi mana sakayya."
Na ce." Amin Mamana, ai babu godiya a tsakaninmu mijina ne kuma shi ma ya yi mini tarin alheran da ba zan iya lissafasu ba ni ya kamata ace na tsaya kan gaba wurin bashi kulawa."
Ta dinga fad'in." Hakane wannan Amina hakane."
Na dan yi shiru ina jinta da kuma nazarin  maganganun da na furta wata zuciyar tana gaya mini kamar na yi mata rashin kunya akan dan uwanta ina cewa ni ya kamata a kan gaba wurin kula dashi bayan suna raye da ita da mahaifiyarsu can kasan zuciyata kuma na gaya mini cewa babu rashin kunya sai tsage gaskiya domin duk cikinsu ke kin fi amfanarsa kuma abokanan rayuwa ne wanda idan babu daya a tsakani dole kowanne ya shiga yanayi na tashin hankali."
To a daran duk wanda ya cancanta sai da na kira shi na sanar da shi har Babanmu sai da na gayawa ya ce da ni gobe zai zo ya duba shi tunda nan nan ne  bunkure.
Aikuwa sammako su Hajja suka buga a gidan Malam ni dai ina bacci na ji maganganunsu na tashi zaune wanda ya yi daidai da shigowar Hajiya Saratu na saki fuska sosai ta shigo tana fad'in." Bacci ki ke yi Amina."
Na ce." Wallahi kwashe ni yayi ban yi tsammani ba Mamana ina kwana ya hanya."
Ta amsa da kulawa sosai tana dan kallona da murmushi a fuskarta.
Hijabina na zura a jikina muka fito tare Hajja ana ta hira da matan malam har da dariya abinda ban taba gani ba duk zuwan da suke yi.
Muka gaisa sosai da ita ina ta mamakin ganin yadda ta watstsake har take ta magana haka.
Rabi'u ya zo suka gaisa kafin ya ce Malam yana magana."
A wannan karon ma tare muka shiga d'akin malamin yana ta k'amshin turaran wuta na tsinke kamar dai koyaushe tsaf ko'ina babu kazanta balle abubuwan da zai nuna malamin matsubbaci ne. Al'kur'anai ne gasu nan a jikin bango a rataye a cikin jaka gefan buzunsa kuwa tarin littafan addini ne masu yawa da irin carbin nan zabgege mai dubu.
Yana zaune cikin tsafta da shiga ta Kamala yayin da majinyacin nasa yake can gefe zaune a kan shimfidar da aka yi masa amma sun dan sanya fillo sun tokare bayansa. Yana sanye da wata babbar riga ta shadda wadda take nuna alama ta malamin ce ita kadai ce a jikinsa sai dogon wando don daga cikin rigar ma ana gano fatar jikinsa sai dai fa gilashin nan nasa na bala'i yana idonsa wato komai d'an lafiya ne.
Shi ma al'kur'anin ne a hannunsa lokacin da muka shiga har da shi wajan amsa sallamar mu gabad'aya hankalinmu na wajan da yake haka zalika shima idonsa na kanmu na yi kokarin daidaita nutsuwata sosai domin yadda zuciyata take ingizani zuwa wurinsa sai nake ganin hakan ba daidai ba ne kada za'kewata ta yi yawa. Amma zahiri Ubangiji ne kad'an yasan yadda nake jin wani mugun dad'i da k'aruwar sonsa a cikin zuciyata. Tunda muka had'a ido sau daya na yi k'asa da kaina smma na saki fuskata sosai a haka muka gaisa da Malamin na zauna gefan Hajja yayin da nake saurarar

maganar da suke yi cikin jin dadin yadda Ubangiji ya sassauta lamarin ya kuma kawo sau'ki cikin dan kankanin lokaci har yana fad'in zuwa gobe ma za mu iya tafiya gida tunda jiki ya yi kyau domin ya cigaba da gudanar al'amuransa."
Hajiya Saratu ta nufi wajansa ina jin suna magana ban dai ji komai ba smma yanayinsu gabad'aya ya ba ni tausayi kwarai da gaske kaina a kasa na ga Hajja ta tashi itama ta tafi wajensa. Na kasa tashi har sai da malamin ya ce mini malama Aminatu je ki duba maigidanki."
Na yun'kura na tashi da tahamidi domin duk motsin da zan yi a yanzu godiyar Allah ce.
Na d'an tsuguna gefan kafafunsa ina fad'in." Baba ya jikin Ubangiji Allah sanya kaffara ce, Allah Ya warware ya kara maka lafiya."
Yana kallona ya ce." Amin Amin Ya hayyu ya 'kayyumu." Hira suke yi a tsakaninsu kaina a k'asa ba zato na ga ya kamo hannu na sai na dube shi da sauri muka had'a Ido sai ya saki hannun da sauri yana duban su Hajja to mantawa ya yi da suna wajan oho kuma sun ga ni da ri'ke hannun da sakin da ya yi kamar wanda ya kama wuta.
A zuciyata na ajiye hakan da kewa da kuma yadda yake jina a ransa.
Da yake kusa da k'afafunsa na zauna sai ya d'an dinga sanya k'afarsa daya yana ta'bo ni idan na kalleshi sai ya yi mini murmushi na d'an janye kad'an ina mamakin abinda yake yi gashi magana suke yi a junansu amma hankalinsa na kaina gabad'aya har sai da suka fahimta ganin hakan ya sanya ni saurin tashi ina fad'in." Hajja sai kun fito."
Ta ce." To Amina ai yanzu za mu fito mu tafi gabad'aya domin Uwani tana kan hanya ba ni so ta zo ba ta same ni ba d'azu da wurwuri kafin mu fito ta kira waya tana gaya mini.
Na ce." To Allah Ya kawo su lafiya."
Kafin na fita sai da na d'an risina gaban malamin tukkuna sannan na fice zuciyata cike da tunanin abinda ya yi wato shi dai mai hali baya fasawa amma in ba haka ba a gaban mahaifiyarka ma ba za ka saurara ba kuma kai da kwana daya kacal da tashinka......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin

neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*

*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*

*07084653262 ko*

*08089965176*

*SIYAN NAGARI!!!!!!*

*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure paid book 2k complete on telegram. What'sapp group 1k Ko kuma arewaa arewa pen*

*0542382124...... Binta Umar Opey bank*

*07084653262*

*130*

Wayata na duba lokacin tara da arba'in da biyar na safiya Lallai yadda ya tashi garau din nan yana da kyau ya sanya sabbin kaya gobe idan Allah Ya kaimu da rai da lafiya. Muna harkar huluna da takalma sosai next target dina bude shagon yaduka da shaddodi in sha Allahu amma dai yanzu ya zama lallai a nemi k'wararran tela wanda ya iya d'inki sosai ya yi masa orgent akwai su k'wararru muddin da kudi yanzu za ka ga biyan buk'ata. Koda Hamusu ya d'aga wayar bayanin da nayi masa kenan ya ce in sha Allahu yanzu zai fita zuwa yamma zai kira ni na ce babu matsala.

Wanka na yi na shirya sannan na zauna na karya da kunu da wainar gero na ji dad'inta sosai dalili na jima ban ci taba kwanciyar hankali da nutsuwar da na samu ya sanya d'andanon bakina ya d:an dawo har ina jin bambacin sukari da gishiri. Gama karin kummalona ke da wuya su Hajja suka fito da

shirin tafiya kafin su tafi din mun d'an jima muna magana tukkuna suka yi sallama da iyalin malamin suka kama hanya suka tafi.
Ashe anti Yagana tun jiya da daddare ta zo garin sai da ta kira ni a waya yanzu na sani tana gaya mini sun shirya tsaf yanzu za su taho su uku ita da Babanmu da kuma Ummansu Hadiza. Na ce kawai su bari idan mun dawo sai su zo gidan Hajja tunda nasan lallai nan za mu zauna kafin ya sake warware mu koma abuja. Na yi mata cikakken bayani sosai yadda za ta fahimta tunda Allah ya tashe shi to sau'ki ya zo ga kowa Kamalu  ma ya ce mini suna so su zo hana su zuwa na yi na ce su bari gobe za mu dawo gabad'aya.
Yinin ranar ana ta shige da fice d'akin malamin yau ya lamuncewa kowa tun daga kan matansa 'ya'yansa duka da surukansa babu wanda bai shiga ya duba shi ba.
Da yamma na nemi Sukairaju domin mun yi waya da Hamusu cewa ya gama had'a mini komai saboda na sau'kaka masa tafiya nace ya bari Sukairaju ya zo ya kar'ba tunda shi da mota a hannunsa. Tsakanin k'waryar birnin kano da k'auye bunkure bai zai wuce awa daya da rabi zuwa biyu ba.
Misalin biyar na yamma ya kama hanya ya tafi bayan magriba da kad'an ya dawo da sa'kon.
Duk abinda na umarci Hamusu ya yi mini yakan yi kokarin yin iyakacin bakin kokarinsa kamar yadda na buk'ata din shadda ce kalar sararin samaniya dakakkiya zanenta irin na manyan mutane dinkin ma fitacce ne da hula zannar bukkar ta karshen tsada da takalmi daidai kafarsa maigidantsaya kamar dai yadda na gaya masa ga yadda nake so.
Na ji dad'i sosai bayan isha'i dana nutsu na kira shi a waya ina sake yi masa godiya sai hakan ya bashi dariya da mamaki yana fad'in abinda ya yi bai kai na yi masa wannan godiyar ba nafi karfin haka a wajensa.
Na yi murmushi kawai  na kashe wayar cikin zuciyata nake
fadin lallai da matasan samari irin Hamsu za  su zama masu tsoron Allah da Amana da an rage masu zaman banza. Hamusu tun kafin na kai k'arfin haka yake tsaye akan dukiyata ban ta'ba kama shi da zamba cikin aminci ba ko ya danne mini kudi duk shekara muke buga lissafi a fitar da abinda aka zuba  a fitar da ribar da aka samu a biya duk wanda yake da hakki hakkinsa. Yanzu da su Kamalu suka koma can al'amarin sai ya kara bunkusa Hamusu na kula da shagon zannuwa da ma'aikatan da suke yi mana d'inki shi kuma Usaini na kula da shagon da muke harkar huluna kala daban daban. Yayin da muka bude sabon shagon sayar da takalma cikin kasuwar kwari wanda Yusi da Saminu suke kula da shi Kamalu kuma hankalinsa ya fi karkata wajan yawon neman sani akan abinda ya shafi da'awa da hadisai Annabi s'aw shikkenan yawon bin malam sunnah yana kuma zuwa legal kwalejin addinin musulunci.

Cikin matan gidan na zauna kamar jiyya muna ta hira sosai suna ba ni sha'awa ganin yadda suke gudanar da rayuwarsu a sau'kake ba kuma su zafafa kishi ainun irin na wasu matan k'auyen ba.
Kayan suna kusa da ni Malam Rabiu yana shigowa na sanya Hajara ta yi mini magana da shi kafin ya shiga bangaransa ya zo muka gaisa sannan na bashi kayan tare da gaya masa na Yallabai ne.

Bai jima ba a wurinsa ba kuwa ya fito da kayan a hannunnsa ya nufi sashen malamin da d'an sauri.

A daran ranar na yi bacci sosai irin wanda na kwana biyu ban yi shi ba hakan kuwa baya rasa nasaba da nutsuwar da na samu da asuba da na yi sallah ban koma ba.
Gari yana yin haske Hajara ta shigo da abin kari da kuma kayan makarantar boko a jikinta litiinin ce dama muka gaisa ta ce Inno ta dora mini ruwan wanka ita zata tafi makaranta.
Na ce ." To na gode sosai Hajara sai dai za mu tafi baki nan kina makaranta ko?"
tana murmushi ta ce." Eh shiyasa na shigo mu yi sallama wata'kila kafin na dawo kun tafi Allah ya tsare ya kiyaye hanya."
Na amsa da Amin Ya Allah. Har ta juya zata fita na kirata ta dawo na ce." Ajinki nawa ne?'' ta ce." Aji na uku a sakandire."
Na gyad'a kaina jakata da take saman katifar dake shimfide a d'akin na d'auka ina da kudi a ciki dubu biyar na mik'a mata ta nok'e wai ba zata kar'ba ba tana dariya ta juya zata fita na tashi da sauri na ri'ke hijabinta jakarta ta makaranta na saka kudin ni ma ina dariya na ce" Ki dinga sayan aya da rake a makaranta na gode sosai kin ji, Allah Ya ba ki miji nagari."
Ta amsa da Amin tana jin kunya ta fita da sauri.
Sai da na karya tukkuna na yi wanka na shirya tsaf na fita domin gaisawa da matan gidan da kuma bankawana.
Malam Rabi'u ya zo yana gaya mini Malam na kira na. Na bi bayansa cikin nutsuwa dama kuma da hijabina a jikina.

littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Koda na shiga d'akin alamu ya nuna mini tare suka yi karin kummalo da malamin domin kayan karin na gani a gabansu sun gama suna magana. A nutse na zauna gefe d'aya na dubi malamin na gaishe shi ya amsa da kulawa kafin na juya shi ma na gaishe shi muka had'a ido. Sosai ya yi mini kyau cikin kayan ya yi fes dashi kamar sabon ango duk da shi din ma'abocin gayu da tsafta ne amma sai nake ganin yau ya fiye mini koyaushe kyau da kwarjini.
Na ce." Baba ina kwana ya jikin." Ya amsa da sauki alhmdullhi."
Na janye idona daga kansa don ganin shi bashi da niyyar janye nasa wasu lukutan idan yana yi mini irin wannan kallon nakan ji nauyi da kunya akan kaina balle kuma da mutane a wurin.
Cikin nutsuwa ya fara yi mini bayanin rubutu da daurikan magunguñan da suke gabansa. Rubutun cikin wata jarka ne yayin da daurikan maganin ya kasance uku daya asha da zuma kullum da safe daya kuma a tsiyayi rubutun kofi daya a zuba karamin cokali sai ya sha idan zai kwanta. dayan kuma a ruwan wankansa za a zuba duka tsayin sati hud'u. Ya sake d'auko wata madaidaiciyar jarka itama cike da rubutu shi kuma kullum da daddare idan zai kwanta za a shafe masa jikinsa da shi.
Sosai ya yi mini bayani ya kuma ce mini na kula kada a tsallake rana d'aya.

Godiya da ni dashi muka dinga yi wa malamin har sai da ya dakatar damu yana dubansa ya ce." Har yanzu a matsayin uba nake a wurinka shin ko ka manta ala'ka da dangantakar da take tsakanina da mahaifinka. Godiyata ga Allah da Ya sanya ina raye wannan kaddara ta same ka. Allah Ya lamunce mini da taimakonsa aka samu mafita don haka tsakanina da kai babu godiya Tajuden yadda zan tsaya akan matsalar yarana hakan nan zan tsaya akan matsalar yaran abokan k'uruciyata."
Wannan kalaminsa ya kashe mana jiki  gabad'aya muka yi sallama da shi muka fito
Wannan karon ma ya tsaya tsakiyar tsakargidan kamar wancen lokacin da za mu tafi yana yi wa iyalin malamin sallama.
Na shiga d'akin na fito da 'yar akwatina ina fad'in." Mun gode sosai Allah Ya saka da alheri Allah Ya biya ku da aljanna."
Gabad'aya suka dinga amsawa suna yi mana fatan alheri kamar koyaushe ya riga ni fita na bi bayansa Inno har bakin soro na farko ta rako ni tana fad'in." Allah Ya tsare ya kuma kiyaye hanya Hajiya Amina."
Yaransa suna jikin mota a tsaye sai suka ba ni tausayi ganinsu a jeme kwana biyar da tufafi daya a jikinsu ko sun yi wanka shi suke yi mayarwa abin ya ba ni tausayi ainun. Amma kuma kallo daya za ka yi musu ka ga annashuwa da farinciki a fuskokinsu sai washe baki suke yi suna sallama da Malam Rabi'u da ya biyo bayanmu. Sukairaju ya bud'e masa motar amma bai shiga ba ya tsaya suna magana da Rabi'un ganin haka ya sanya ni shiga na zauna kimanin minti biyar ya shigo da Bismillah  a fuskarsa.
Ajiyar zuciya na sauke bayan mun hau titi na dan lumshe idona ina ambaton sunan Allah Ubangiji Allah kada ka kara maimaita mini wannan tashin hankalin da shiga.
Har muka isa gidan Hajja bai fi sau hud'u muka yi magana ba dalili akwai yaran shi don Sukairaju ma yana daf da shi shiyasa ya kama kansa ya dai gaya mini cewa shi ya hana su Hajja zuwa ayau din ita a yadda ta so su zo sai mu sake juyawa tare.
Kawunansa biyu muka samu a gidan Hajja Alhaji Sa'idu da Alhaji Haruna wanda shi baya gari ma al'amuran suka  faru sai da ya dawo tukkuna ya samu labari.
sai kuma Inna Uwani ita kad'ai ce ban ga Hauwa ba sai 'yar uwarsa Hajiya Saratu.
Sun d'an jima tare da shi suna tattauna mas'aloli da yawa kafin su tafi.
Shi ma ba su jima da tafiya ba ya tashi yana fad'in zai shiga ya kwanta gidan tunda yana da wajensa na mussaman a gidan wanda ya shirya shi domin yin rayuwa da matarsa ta farko Samira Allah bai kaddara zama ba.
Ina Uwani ta kasa yarda mu had'a Ido ban san dalili ba daga zarar na daga kaina ana hira sai ta yi saurin sunkuyar da kanta kasa na dinga tunani akan abinda yasa take yin haka. Har dai abin ya zo yana ba ni dariya babu mamaki tana jin kunyanta ne da tsoron kada na tona mata asiri a wurin yar uwata tunda yanzu an yi walkiyya asirin Hajiya Maryam ya tono to ita kuma tasan na ganta da idona tana yarfa masa ruwan rubutu mai d'auke da magani a hanyar wucewarsa a shekarun baya. Cikin zuciyata nace jininka ma

yana yun'kurin cutar da kai ina ga kuma wani daga waje wanda yake karyar so. Ai soyayya ta gaskiya itace ka so mutum tsakani da Allah ka so abinda yake so, ka gaya masa gaskiya a duk lokacin da ya kauce hanya. Ka k'yamaci munanan ayyukan da yake yi kuma ka yi kokarin nuna masa hanyar daidai. Babu wata soyayya ta gaskiya da za ta sanya ka illatar da wanda kake so ta hanyar son rai wannan zalinci ne a so ba cikakkiyar k'auna ba.
Muna nan zaune wajan daya da rabi Yusi ya dawo daga makaranta suna da lakca da sassafe ya fita ba don ya so ba.
Muna gaisawa yana tambayata ina Baba. Hajja ta ce ya fita harabar gidan Sukairaju zai nuna masa inda yake. Aikuwa ya tashi ya fita da sauri anan ya bar tarkacensa na makaranta ya fita da sauri bai damu da tsokanar da ake yi masa ba.
Ni hakan bai ba ni mamaki ba tunda na dade da sanin matsananciyar soyayyar da take tsakaninsu. Shi Kamalu baya ma garin gabad'aya a jiyan da yamma suka tafi Abuja wurin wannan malamin professor Ma'kari.
Da yammacin ranar dai ya tura Sukairaju can gidanmu na sharad'a da kayan shi a can ya d'ebo masa duk abinda ya zama lallai zai buk'ata a son ransa mu tafi can mu biyu Hajja ta ce a a mu zauna anan din na tsayi sati tukkuna ko sati biyu idan ya so idan ma abujan za mu koma shikkenan.
Ganin haka sanya ni sanar da Sahura tunda ni ma ina da kaya a can ta sake d'ebo mini. Na kira Hamusu na ce masa ya sayi yaduka masu matsakacin kudi kala bibbiyu ya bayar da d'inki Sukairaju da D'ahuru da kuma Ade ya san biyu Ade din ne bai sani ba na ce shi ma ba shi da tsayi sosai Amma dai duk ya fi su ki'ba da kad'an. Na tausaya musu da zama da kaya daya babu dadi kamar akwai cutarwa.

A daran ranar na fara ko'karin yi masa amfani da rubutu da magunguñan da malamin ya ba shi tunda ya jadadda mini sosai kuma a gabansa. Babu matsalar zuma ya had'a da ita gangariya ce farar sa'ka wannan da safe ya ce ya sha kafin ya ci komai.
Da za mu kwanta ne a lokacin da za a shafa na shafawar a duk jiki na ga shegantaka ya cire jallabiya har da gajeran wandon ya zauna a haka na ce babu kyau kallon tsaraicin mutum ya ce ai yana jin lokacin da malamin ya ce sai babu komai a jikinsa za a shafa rubutun har yana kara jadaddawa ya ce ki shafe mini ko'ina na jikina.
Ya kwanta abinsa babu kunya ba tsoron Allah da jin nauyin abinda ya yi. Na jima kaina a sunkuye da rubutun a hannuna. Ba wai shafawar ce matsala ba yadda zan kalle shi a haka shine damuwar na tashi na je na kashe fitila na dawo da lalube na zauna na fara shafa masa a haka a cikin duhun. Bai yi yun'kurin yi mini komai ba har na gama bai kuma yi magana ba a takaice na ce." Na gama.'' Ya lalubi wayarsa ya kunna hasken yana ko'karin tashi zaune na d'auki wandonsa na ciki na bashi ya sanya sannan yasa jallabiyar ya koma ya kwanta.
Sai da na yi wanka da alwala tukkuna na kwanta gefansa wanda duk a tunanina bacci yake yi. Ya janyo ni sosai ya rungume tsam. Haka muka kwana bai yi yun'kurin yin wata mu'amula ta aure da ni ba sai dai duk juyi

zai sake rike ni a jikinsa ya sanya bakinsa wuyana ya sumbuta da haka har asubahi ta yi muka tashi kusan a tare......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Littafin kudi ne akwai complete 2k a Telegram normal What'sapp group kuma 1k akwai a arewa pen domin biyan kudin karatu......0542382124....Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*131*
A ranar da muka wayi a gari a gidan Hajja muka dinga kar'bar mutane mababambamta ciki har da su anti Yagana Babanmu da Sahura wadda ta kawo mini kayan dana ce ta d'ebo mini.
Babanmu dai bai wani dade sosai ba ya tafi babu yadda ban yi da shi ba akan ya zauna ya huta ya kuma ci abinci sai asa direba ya mayar dashi gida ya ce a a tafiya zai yi ba zai zauna ba. Ina jin dadin yadda yake ko'karin kama mutunci da kuma girmansa ba ya ta'ba yadda ya yi abinda zai zubar mana da mutunci gabad'aya.
Yini muka yi tare da su anti Yagana Ummansu Hadiza da Sahura ana ta hirar duniya Ummansu Hadiza dai ta yi shiru kanta a kasa sai dai ta yi d'an murmushi yanayinta gabad'aya babu dad'i zantukan da su anti Yagana suke yi akan Hajiya Maryam da irin zagi da tofin alatsinen da suke yi mata shine ya dan dameta wata'kila tunda itama tana ta'ba harkar bin malaman yasa ta damu tana ganin kamar anti Yagana da gayya take zage-zagen tun muna yara muka tabbatar da hakan yanzu ne da duniya ta juya mata baya ta gane babu sarki sai Allah ta daina, to babu kudin yi ma a yanzu amma ba zan ta'ba mantawa ba ita har zannuwanta take sayarwa ta tafi wajen malami.
Sai yamma Garba ya d'auke su a mota domin mayar da su gida ina jin anti Yagana tana gayawa Hajja za ta sake dawowa kafin ta tafi domin da Hajjan cewa ta yi wai su zauna su kwana.
To ita Sahura da mijinta duk da har yanzu ba wai sun shirya ba ne ta dai koma amma a yadda take ba mu labari ta'ki sakin jiknta da shi har yanzu kuma shi bai fasa shirye-shiryen auransa ba da ya rage wata biyu a daura tunda budurwa ce yarinyar da zai aura.
Shine fa take gaya mata cewa za ta dawo kafin ta tafi wanda ni nasan ta fadi hakane kawai amma ba dawowar za ta yi ba.
Kwananmu hud'u a gidan Hajja mutumin ya warware sosai ya ma fara fita yana duba ma'aikutunsa nan yana kuma yin baki a kai-akai.
Ranar da muka cika sati daya a gidan Hajja da sassafe ya tafi
bunkure bayan la'asar ya dawo sai da ya yi wanka ya ci abinci tukkuna yake gaya mini wai an bashi sa'ko ya kawo mini. Na ce sakon menene ya ce bai sani ba yana mota wata yarinya ce wai Hajara dariya na yi ina fad'in." Ai k'awa na samu a gidan.
Ya gyad'a kansa bai ce komai ba. Can kuma ya ce gobe za mu tafi Abuja Amina hankalina na kan yara.
Na d'an yi shiru Ina kallonsa mun yi waya da Kamalu shekaran jiya tunda yana garin tare da ayarin abokansa masu neman da'awa. Ya ce mini ya je gidan domin duba yaran suna nan lafiya lau har Hauwa ta ba shi turare.

Mamaki na yi sosai Hauwa ta koma kenan amma ba ni tsammanin iyayen sun sani da shi mai gayya da aikin da ko maganarta ma baya yi. Kenan idan tana gidan a ganina yaran ba za su yi kad'aici ba fad'in haka daga wajensa ya tabbatar mini da cewa bai san cewa ta koma ba. Yadda bai san lokacin da ta tafi ba haka zalika ta koma bata gaya masa ba ya makomar auran na su take ni dai har yanzu daga wajensa ban ji wata tartibiyar magana ba. Amma na tabbatar da cewa ba zata koma ba tare da sanin mahaifiyarta ba.
Na ce masa hakan ya yi ni ma hankalina yana kan yaran yanzu duk da nasan ba su da wata matsala dalilin samun k'wararriyar mai raino.
Tun bayan tashinsa yau sati daya kenan bai ta'ba neman yin sunna da ni ba sai dai yakan rungumeni ya tatta'ba abinda yake so a jikina har mu yi bacci a wanda ni kuma hakan ya kan jefa ni yanayi na damuwa da buk'ata dalili sha'awata takan motsa sosai na shiga wani yanayi na gigita. Ban ta'ba kawo cewa matsala ba ce sanin da na yi masa gwarzo ne sosai a wannan gefen jajurtacce ne wanda duk fitinar mace yakan k'ureta.  Sai a yau da muka lula cikin shau'kin da muka kwana biyu ba mu riski kanmu ba a ciki ba. Sosai muka kai k'oli a lokacin ya yi ta ko'karin ganin mun yi kamar yadda muke yi amma abin ya ci tura ya fara da k'umaji da karsashi amma kash jim kad'an jikinsa ya mutu ya gaza tab'uka komai na yi iyakacin yina domin ganin mun cigaba da nemawa kanmu mafita amma hakan bai samu ba k'arshe ma kirif mirginawa ya yi ya kwanta gefena ya kama bacci abinda bai ta'ba faruwa ba kenan.
Na tashi zaune tare da sanya rigata ina kallonsa gabana na faduwa. Me yake Shirin fad'uwa kuma. Tarihin rayuwata dashi babu ranar da ya ta'ba gaza mini a shimfida duk yadda nake ji da fitina ya fi ni, koyaushe ma cikin kirkiro abubuwa yake yi wanda yake jefe ni d'imauta da shau'ki.
Kasa ha'kuri na yi sai da na tashe shi ya tsarkake jikinsa tunda ka'idarmu ce ni da shi ba ma kwanciya sai da tsarki.
Da safe duk yadda ya so ya danne damuwarsa sai da fuskarsa ta nuna abin shima bai yi masa dad'i ba.  Na yi ta nazari akan abinda ya faru a jiyan shin asirin ne bai sake shi ba ko kuwa wata sabuwar matsalar ce ta kunno mana.
Da rana da kaina na bashi abinci a baki da yake towon shinkafa miyar taushe ne idan na gutsiro nasa masa baki sai ya had'a da yatsuna ya tsotse a haka ya rikita ni sosai ina daurewa har sai da yanayina ya canza gabad'aya kwanciyar nan tasa ta sanya shi k'aro fitintinu fannin romance. Amma kuma kamar wanda aka dasa wa tsoron  yin auratayya da ni. Haka muka ciyar da juna abincin kamar sababbin amare muna ta soyayya muka sake hawa gado nan ma abinda ya faru jiya da daddare ya sake kasancewa. Da mazantakar sosai irin ta d'a namiji yake dumfarata amma jim kad'an da farawa sai ya yi realizing jikinsa ya mutu!

Gudun aure littafin kudi ne Hajiya kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ni dai kamar zan yi dan k'aramin hauka na fashe da kuka ina kallonsa a kwance gabad'aya hankali ya tashi ban ta'ba cikin da ya sanya ni masifar son jima'i ba tun yana karaminsa sai wannan.
Ya tashi ya kamo ni ya riga ya gane akan abinda nake yi wa kuka na kasa daurewa domin abin sabo ya zo mini abinda nake ci na ture amma yanzu ana dan sammi ni kad'an wanda yake tayar mini da kwad'ayina. Ya fara kici-kicin ko'karin sake jarrabawa babu ma mazantakar kamar ta farko ban kuma ji abin yaje can har inda ya cancanta ba. Hawayen takaici ya dinga ziraro mini ta gefen ido. Ya gama jagwalgwalani babu biyan buk'ata ya sauka shima kamar ya d'ora hannu aka ya kurma iho ya shiga bandaki.
Na tashi zaune rungume da bargo a jikina na kasa danne kukan yin sa nake yi tukuru domin gabad'aya jikina ya riga ya nuna ga abinda yake buk'ata kuma bai samu ba. Ina da sha'awa daidai misali amma abin ya kara tu'azzara sakamakon cikin da nake d'auke dashi wanda shi bai ma san da shi ba.
Ya fito ya same ni a haka ya sanya kayansa ina zaune yana fad'in."Kin ga halin da na tsinci kaina a ciki ko Amina."
Na dube shi ina jan hanci ban ji haushinsa ba sanin da na yi ai da ba haka yake yi ba tabbas akwai matsala ko asirin ne har yanzu bai gama rabuwa da shi ko kuma dai wata matsala daban.
Na ce." Kai me kake tunani da hakan?"
Ya d'an yi jim kafin ya furta." Jiya zuwan da na yi bunkure yana da ala'ka da hakan Amina aikin da Maryam ta yi wata'kila har da wanda zai hana ni mazantaka da gamsar da iyalina wace irin masifa ce wannan Amina? Maryam ba sona take yi ba wannan mugunta ce."
Ya kàrasa maganar kamar zai rushe da kuka har da 'yar kwalla a idonsa.
Na ce." To yanzu me malamin ya ce?
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Zan cigaba da amfani da magunguñan da ya had'a mini da farko ai yau kwana takwas kenan kuma na sati biyu ne idan na kammala ya ce sai na yi magana da shi domin tabbatar masa da cigaban da aka samu. Amina na fi ki shiga tashin hankali domin ban shirya rabuwa dake ba"
Ya riko hannuna ya matse sosai yana fad'in." Ko mu k'ara jarrabawa yanzu?"
Da sauri na girgiza kaina na ce." A a mu bari ka gama amfani da maganin da rubutun sai mu sake gwadawa amma ka daina maganar rabuwa ba zan iya ba ni ma."
Ya d'an rungomo kafadata yana fad'in." Ji bi kukan da ki ke yi fa Amina nasan wacece ke tsakanin jiya da yau ke kadai ki ka san halin da kike ciki tun d'azu da muna cin abinci na fahimci damuwarki."
Na sanya hannu da sauri na goge kumatuna ina fad'in." Ka daina fad'in haka ni ba wannan ne damuwata ba yadda abubuwa suke ta faruwa da rayuwarka shine abinda ya fi daga mini hankali."
Ya yi murmushi yana cewa." Kin fadi hakane kawai Amina ko da wannan to ba shine musabbabin sanya ki kuka tuk'uru ba. Idan ba kya samun gamsuwa da ni ai akwai cutarwa ko?"
Yafad'a cikin rauni wanda ban ta'ba ganinsa a ciki ba. Hawaye ya sake ciko mini ido na ce." A a fa na gaya maka ba haka ba ne."

Shiru kawai ya yi bai ce komai ba yana dai ta murza hannuna da ya rike.
Na dago na dube shi a tsanake ina fad'in." Wannan matar ba sonka take yi ba idan har haka aka so to Allah ya wadaransa ba zan yafe mata ba."
Ya ce." Idan ta karya karsashina na d'a miji za mu tsaya a gaban Allah da ita Amina wallahi tallahi ba zan yafe mata ba ni ma."
Ya fad'a da masifar damuwa. Cikin wannan yanayin kira ya shigo wayarsa ya cika ni ya tashi.
Ni ma na d'auki rigata na sanya na nufi toilet na ji yana fad'in.'' E, gobe nake so na tafi Abuja a alhamdulillahi fa jiki da sauki wallahi, amma tunda ka ce za ka zo za mu jira ka in sha Allahu."
Na shige na je na tsarkake kaina ina fitowa yake gaya mini da Baban Saude suka gama waya yana tafe.
Na ce." Ka gaya masa baka da lafiya ne?"
Ya ce."  Ya kira wayoyina lokacin da nake kwance a bunkure Bai same ni ba sai shekaran jiya ya sake kira yake gaya mini yana ta neman wayata bata shiga har taki ma ya kira bata tafiya a lokacin na ce masa  na kwanta jinyya ne wallahi,  ya yi fad'a sosai wai da mutuwa na yi ashe sai dai ya ji labari ba za a gaya masa ba.''
Na ce." Gidan malamin fa akwai matsalar network sosai ni kaina sai na yi da gaske wataran nake samun damar kiran waya  amma idan ya zo sai a ba shi ha'kuri ko?"
Ya ce." Haka za a yi domin wannan Baban namu rigimamme ne, koda yake ai ya fara tsufa ba za a rasa shi da rikici ba."
'Dan hararsa na yi na ce." Zan kuwa gaya masa idan ya zo to dame kwado ya fi gaya kaima ai ka fara tsufan Baba."
Yana dariya ya ce." Ke ma haka malama kin tsufa kawai gaya miki ne da ban yi ba."
Ta'be bakina na yi ina cewa." To menene a ciki tsufa dole ne fa kowa ya tsufa kuma darasi ne."
Ya gyad'a kansa tare da janyo hannuna na zauna a gefensa ya ce." Ina kallon ki a matsayin matata har a cikin aljanna. Abokiyata makusanciyata da babu wani shamaki a tsakaninmu Amina me ki ke ganin ya cancanta da Malam 'Daha umara dai na bashi shi da Rabi'u in sha Allahu da azimin nan da za mu shiga amma bayan wannan ina so na yi masa alheri wanda zai nuna masa cewar na yi alfahari da taimakon da ya yi mini a ganina kudi sun yi kad'an wajan biyansa wannan hidimar."
Shiru na yi Ina nazari lallai Malam D'aha ya cancanta da ayi masa komai dalilin namijin ko'karin da ya yi har yanzu ma yana kan yi. Na ce." Ka sanya a rushe gidansa tsaf tunda na ga na kasa ne ginin da a zamanantar dashi  a gyara masa tsangarsa sannan ka samawa wasu daga cikin yaransa maza aikin yi ko da a karkashinka ne duk da zaman da muka yi a gidan na fahimci ba su da yunwa dalili duka yaransu suna fita gona amma yana da kyau a ce sun fito cikin gari sun waye sun dan yi karatun zamani da hurd'a da jama'a da kasuwanci."

Ya dinga gyada kansa yana saurarena har na gama maganata ya ce." Haka za a yi my love shawarar nan taki ta yi mini sosai za a yi duk yadda ki ka ce in sha.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

Masu buk'atar a tallata musu hajarsu kofa a bud'e take za a yi akan farashi mai sau'ki in sha Allahu rabbi

*Gudun aure paid book ne 2k complete on Telegram normal What'sapp group kuma 1k ko AREWAPEN via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*132*
Baban Saude dai lokacin da ya ji abinda matar da yake yabawa ko'kari da bajintarta ta fannin kula da miji har ma yana bada misali da ita tare da jaddada goyon bayansa akan abinda a gaya masa a kanta sai da ya ki'dime sosai. Mutum ne shi jarumi jajurtacce wanda ko rasuwa aka yi bata gigita shi ainun domin ko lokacin da Mamanmu ta rasu ya nuna jarumta da dakiya a cikin 'yan uwanta ko yanzu a ka tashi zancenta yana tsawatarwa da masu yi mata kuka cewa ba daidai ba ne sai ga shi jin irin mugayen ayyukan da maccen da yake misali da ita tare da ko'karin tabbatar mata da aljanna ta aikata ya yi shiru yana zare ido har abin ya so ya ba ni dariya na danne ban yi ba. Da farkon da abokin nasa ya fara bashi labarin ya dinga dakatar da shi yana nuna babu yadda za a yi ta aikata haka tunda shi kansa ya sheda soyayyar da take masa a ganinsa babu dalilin da zai sanya so ya sanya ka nakasta wanda kake so. Ganin yadda yake rantse masa da girman Allah da buwayarsa ya sanya jikinsa saduda ya yi tsuru kawai yana saurararan bayanin da yake yi masa da yadda ya ci tsananin wahala kafin ya samu kansa a yanzu da yake zaune suna magana.
Ya jima yana girgiza kai da tu'ajibi da mamaki kafin ya bud'e bakinsa yana fad'in an yi shed'aniya amma mai suffar munafukai tana sunkuyar da kai kamar mutuniyar arziki ashe macijiya ce mai mugun dafi Allah Ubangiji ya saka muku da mu kanmu da ta jefe cikin zullumi da tashin hankali da damuwa.
Da k'yar da jibin goshi ya yarda ya kwana a gidan Hajja a cewarsa zai je ya kama hotel idan ya duba Baba Sule a asibiti sai ya d'auki hanya da sassafe tunda jibi zai komai bakin sana'arsa.
Da 'kyar ya lalla'be shi ya amince.
Da daddare gabad'aya har da ni muka je asibitin domin duba jikin Baban Sule kamar dai yadda ya fad'a.
Alhamdulillahi jikinsa da sauki wai ashe basir ne yake damunsa irin mai daure cikin nan. Ya yi tsiro kuma yana fitar da jini sai da aka yi aiki duk ya rame kuwa ya zabge kamar ba Baba Sule ba Sunusi babban d'an sa shine yake jinyarsa.
Na tausaya masa sosai kuma ban san haka ciwo ya ci karfinsa ba duk da ba ni cikin hayyacina amma ina da hakki a sanar mini domin na bada taimakona asibitin gwamnati ne amma dole ai za a sayi magani shi kuma bashi da k'arfi asalin ubangidansa Alhaji Muntari ne kuma ya rasu don ma yaransa maza sun tashi sune suke ta dawainiya da shi da taimakon Babanmu tunda alhamdulillahi yanzu shine yake da rufin asirin da ba su dashi tun farkon

samun d'aukakata dana bude masa shagon huluna yake cigaba da gudanar da kasuwancinsa.
Bacci yake yi har muka gama zamanmu a d'akin da yake bai farka ba da za mu tafi Baban Saude ya bawa Sunisu dubu goma ya ce a sayi magani shi kuma Yallabai din ya ce zuwa gobe zai ga sa'ko.
Jin haka ya sanya ni kar'bar lambar wayar Sunusin da ta asusun ajiyarsa nasan lallai tunda ya fadi haka zai buk'aci da na bashi details din da zai saka kudin.
Duk da dare ne ashe da yawa wasu sun ankara da shigowarsa asibitin muna fitowa kuwa jama'a suka rufe shi ni da Baban Saude muka ja gefe muna kallon ikon Allah  uwar zuma kenan ki tashi a biki idan har za ka bayar to babu shakka za ka ga tarin masoya da yawa.
Sukairaju da yake bayansa ganin abin ya yi yawa ya sanya ya fara ko'karin korar mutane muka nufi mota suka biyo mu har da mata masu zaman jinyya.
Mota muka shiga gabad'aya har da shi ya bude ma'ajiyar kudinsa ya fito da kudi da d'an yawa ya mik'awa Sukairaju wani dattijo ya bawa daga ciki ya ce su kasftaa.
Ya zo ya shiga motar da saurin gaske domin ganin jama'a na sake k'aruwa a wajan.
Baban Saude tun a mota yake tsokanarsa wai zai yi kyau da siyasa ya nemi kujera gwaman Kano.
Ya dinga dariya yana fad'in abinda bai taba sha'awa ba kenan siyasa ya yarda dai ya yi gwagwarmayar ta neman kudi a ko'ina ya tara ta hanyar halak amma mafiakasari 'yan siyasar nan da suka ci suka tada kai suna bushasha da dukiyar jama'a suna mutuwa da nauyin al'umma a kan su.
B'angaran ba'ki na cikin gidan Hajja ya sanya Sukairaju ya gyarawa Baban Saude ya kwana anan da sassafe kuwa ya kira shi a waya yana fad'in shifa ya shirya.
Ba shiri muka fito harabar gidan ni da shi sai a lokacin ma muka gaisa aka yi aka yi dashi ya jira aka kawo masa abin kari ya ce a a. Sai da ya yi masa dubara kan cewa yana da kyau ya yi wa Hajja sallama kafin ya tafi sannan ya yarda muka shiga ciki a tare anan Hajja ta sanya aka kawo masa abinci funkaso da miya da kuma kayan shayi ya sha ruwan shayin babu madara sannan na zuba masa funkason manya guda biyar zan zuba miya ya ce na cire biyu na bar masa uku ya isa.
Na yi yadda ya ce din ya sake sosai da Hajja ana hira da shi har aka ta shi labarin abinda ya faru ya kara jadadda mata mamakin da ya yi da aka ce masa Hajiya Maryam mashirika ce duk nagartar da ta nuna masa a farkon ganinta da shi bai taba tsammanin haka daga gare ta ba.
To bayan tafiyar Baban Saude da kad'an ni ina tare da su Hajja a falo muna hira har da ita inna Uwanin shi kuma ya bi bayan Baban Saude amma bai dawo ba.

Littafin kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na ji maganar Hajja cikin nutsuwa tana kiran sunana.
Na amsa tare da mayar da hankalina gare ta ta ce. "Amina."
Na ce." Naam Hajja."
Ta ce." Hauwa ta koma dakinta  tun Tajo yana bunkure a kwance."
Na d'an saki fuskata ban nuna mata cewa na sani ba na ce." Ma sha Allah Hajja ai haka ya fi Allah ya kiyaye gaba."
Ta amsa da Amin Ya Allah. Ta cigaba da cewa ita da mahaifiyarta suka buk'aci hakan ga ta a zaune hakane Uwani?"
Ta amsa "Hakane Hajja."
Sa ta cigaba da cewa." Hauwa a cewarta tana jin kunyarku ke da Tajo bisa abinda ta yi na rashin kyautawa a baya ta yi nadama ta kuma gane ba daidai ba ne. Ta ji labarin ibtila'in da ya samu mijinku shine ta ce tunda ke kina tare dashi kina jinyarsa ita sai ta koma ta kula da yaran. Jin hakan ya sanya na bada goyon baya domin yaran za su samu kulawa sosai kuma za su ji dad'i akan ace suna tare da masu aiki."
Falon ya yi shiru ina sauraran ta cigaba da magana domin nasan ba ta gama ba. Can kasan zuciyata kuma ina mamakin ta hanyar da suka b'ullo wato dama mafaka suke so su samu tunda ta fara gane kuranta tana bibiyarsa yana shareta da ya kwanta ciwo kuma ta tabbatar ina tare da shi ta san yara sun dawo hannuna sai ta lallaba ta koma ta fake da cewa za ta kula da yara da haka suka tsara Hajja har ta amince take kuma ganin sun kyauta sun yi tunani mai kyau.
Babu wata sha'kuwa tsakanin Hauwa da yara har na cikinta domin ba da ita suka rayu ba abinda yake tsakaninsu tsawa ce da hantara wataran har da duka. Khalil dai yana shan rank'washi ko ta kwashe fuskarsa da mari na gani kusan sau biyu. To balle Minal ma da bata son zuwa wajenta. A ganina babu wata mafificiyar kulawar da za su samu a wajenta baya ga ta Mairo da Taburni tunda da su suka saba kuma  duk wata nau'in kulawa suna samu a tare da su.
Ta cigaba da cewa." A wani zuwa da Tajo ya yi nan farkon rikicinsu ya ce mini ya mayar da ita kusan wata hud'u kenan har yanzu tana a matsayin matarsa a yadda na sani dai ban san kuma shi abinda yake zuciyarsa ba sai ya shigo sai na tambaye shi."
Ta Nisa kafin ta cigaba da cewa." Shekaran jiya mun jima da ita a waya sosai na ja mata kunne kada na ji kada na gani ba ni son wata matsala ta sake faruwa idan ta shure maganata zan cire hannuna a kanta kuma zan bawa Tajo za'bi zama da ita ko rabuwa."
Inna Uwani ta yi k'asa da kanta cikin damuwa Amma ba tofa ba.
Na ce." In sha Allahu ma babu abinda zai sake faruwa Hajja, ni da ma tsakanina da Hauwa ai girmamawa ce wallahi kuma na ji dadin wannan sulhu wanda da tun farko ta yi aiki da shawarata hakan ba za ta faru ba, ina yi musu fatan alheri."
Ta ce." Ba wai ina goyon bayan Tajo ba Uwani ki zauna ki yi nazari da tsinkaye anan Hauwa ta yi daidai na yi shiru ne kawai ba wai don abin bai yi mini ciwo ba. Ban isa na bata umarni ta bi ba na sha gaya masu daga ita har abokiyar zamanta a duk lokacin da suka samu sa'bani da magidansu su

sanar da ni, amma saboda ta raina kowa ta haihu da d'anyen jego ta tafi ke kuma ki ka bata wajan kwana har kina aiko mini da sa'ko iyayen Hauwa sun ce a ba su takarda domin su ga sheda."
Inna Uwani tasa kuka tana fad'in." Hajja ni kaina Hauwa taurin kanta ya ishe ni wallahi nasan bata kyauta ba kuma b'acin rai ne ya sanya na fadi haka abinda ya kara dagula mini lissafi yadda ta ce mini yana dukanta kuma ya mayar da ita koma baya a gidansa har hakkinta na aure baya bata shine hankalina ya tashi."
Hajja ta harareta tana fad'in." Baya bata hakkinta na aure a ina ta samu wannan cikin da ta haife wad'ancan yaran biyu Khalil da Minal a ina ta same su?"
Inna Uwani ta yi shiru tana jan hanci tare da goge ragowar hawayen idonta.
Ta gyad'a kanta tana fad'in. "Ai ban 'ki komawar ba domin ban san abinda Allah ya lullube ba, shiyasa tun da farkon faruwar lamarin na tura shi can bauchin domin a samu sasanci ba ni da niyyar raba uwa da yaranta tunda ni ma babu wanda ya yi mini haka. Nasan soyayyar da take tsakanin iyaye da yaransu me yasa na yi masa fad'a sosai a lokacin da ya kwashe musu yara ya kaiwa Hajiya Maryam. Ba daidai ba ne amma dole a wannan ga'bar mu yi masa uzuri tunda ba a hayyacinsa yake ba har yaran gabad'aya nasan yanzu ko giyar wake ya sha ba zai k'ara yarda ya d'auki d'ansa da'ya ya kai wani wajen ba sai dai idan ya zama dole."
Ta girgiza kanta tana fad'in." Hakane wannan hakane."
Ta ce." Ki ja mata kunne kwarai idan za ta ji tunda ta fi karfin ki ba tun yau ba na fahimci haka wannan ya zama na farko ya zama na k'arshe ta zauna ta kula da yaranta."
Ta ce." Ai tun a gida na yi mata fad'a sosai Hajja ai abinda ya fi alheri shine ta koma cikin yaranta domin duk wanda zai rike maka yara ba kamar uwa ba."
Hajja ba ta ce mata komai ba ta juyo gare ni tana fad'in." Ya gaya mini cewa gobe za ku tafi hakan ya yi ba zan dakatar da shi ba domin nasan yana da hurd'odi da yawa. Ki yi hakuri ki 'kara akan wanda ki ke yi Amina ni dai babu abinda zan yi domin na saka miki alherin da ki ka yi mini sai da na ce Allah Ya yi miki albarka ya albarkaci zuri'arki ya sa su zama abin koyi da kwatance a duniya."
Na ce." Wannan addu'ar ita kad'ai ta isa Hajja ai ban yi domin a gode mini ba ni ma kaina na yi wa kuma in sha Allahu ni dai daga bangarena zan yi iyakacin bakin kokarina wurin ganin mun samu zaman lafiya da juna."
Ta saki fuskarta sosai tana fad'in." Na gode sosai Amina Allah Ya yi miki albarka na gode."

To a daran ranar ta kira shi ya je ya same ta nasan dai ba zai wuce maganar da za ta yi masa ba kenan. Ko da ya dawo ya same ni tare da Yusi muna bankawana ban ga wani can ji a fuskarsa ba ya zauna cikinmu ana hirar da shi har yana tsokanar Yusi ya zama saurayi ko yana da budurwa ne shima. Abinda ya assasawa yaron tashi ya fita kenan yana sinne kai shi kuma sai

dariya yake masa yana fad'in." Ta'b wa ya ga su wa'e da suruka  humm tsufa ya zo garinsu wata mata."
Na gane da ni yake na share shi ban tanka masa ba ya cigaba da cewa ni kuwa kin ga ko yanzu zan iya auran budurwa ba ni da matsala.
Ban kula shi ba na tashi na shige band'aki ina murmushi wani sa'in idan yana barkwacin har mamaki yake ba ni.
A wannan daran kafin mu kwanta ya kar'bi details din Sunusi dubu dari da hamsin ya sanya masa ni kuma na sa hamsin a kai ya zama dubu dari biyu ta What'sapp na yi masa magana na ce ya duba sako  an tura masa.
Ya kuwa kira ni a waya ya yi ta godiya kamar zai ari baki.
To duk yadda na kai ga nok'ewa a wannan daran kasawa na yi domin ha'din kai na bashi zuciyata na dokawa muka jima cikin wassanin soyayya ya yi kokari kwarai ta wannan hanyar ya samar mini da nutsuwa kafin ya nemi hanyar biyan tashi buk'atar cikin k'ankanin lokaci yana farawa ya kammala. Akwai sha'awar sosai da mazantakar amma karfin da za a jima ana yi ne babu wannan kuwa babbar matsala ce.
Da sassafe muka d'auki hanyar abuja bayan duka mun yi sallama da wad'anda suka dace....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: *GUDUN AURE PAID BOOK 2K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1K KO KU GARZAYA AREWA PEN.*
*0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*133*
Yadda yaran suka dinga tsalle da murnar ganin Babansu haka ni ma suka yi mini kamar dama can akwai tsananin sabo a tsakanina da su. Minal dama can 'yar gidana ce kai tsaye wajena ta taho da dan gudunta tana tsalle da dariya na kuwa sunkuya na sunkuceta duk nauyinta ni ma ina dariyar murnar ganinsu tsaf cikin annashuwa. twins kuwa dama wajan Babansu suka nufa ya rirri'ke hannayensu shima fuskarsa kamar gonar addu'a Allah ne kad'an yasan yadda yake ji a cikin ransa ganin ya dawo cikin ktoshin lafiya domin cigaba da rayuwa da su. uwa uba kuma samun iyayen rainon da suke tsananin kula da su tamkar suna rayuwa da iyayensu. Yarinyar ta dabaibayeni sosai ta sa'kalo wuyana da hannayenta tana ta dariya duk acikin farincikin ganin mun dawo. Ina nishi sosai gajiyar tafiya da yanayin jikina ga kuma nauyinta na fara ko'karin sauketa k'asa ina kallonsu Mairo da suke tsaye suna ta dàriya na ce." Minal ta kara girma da nauyi a 'yan kwanakin nan Mairo me kike bata?''
Cike da kulawa ta sinne kai ta furta. " Abiñci take ci ta k'oshi Hajiya bayan haka babu komai tunda ita dama can ba gwanar ciye ciye ba ce."
Shiru na yi ban ce komai ba na sauke yarinyar a k'asa tana riko gefan hijabina ina jin Mairo da Taburni suna yi masa sannu da zuwa. Baba Tabawa ta fito daga cikin fuskarta a washe take fad'in." Sannunku da zuwa Alhaji sannuku da dawowa."

Ya tsaya suka gaisa sosai kafin ya kama hanyar samansa yaran suka bi shi a baya Khalil da twins ita Minal tana tare da ni ta ri'ke mini hannu tamau.
Muna magana da Mairo Hauwa ta fito daga d'aki muka kalli juna babu yabo babu fallasa ta furta." Kun dawo kenan?"
A tak'aice na ce." E, mun same ku lafiya?'' Ta amsa da 'Kalau.' Ta nemi kujera ta zauna na d'an dubeta ta gefan ido ta k'ara ramewa abinka da mara jiki dama ai zaman gida sai dole ta so ta yi wa kanta ganganci. Ta yi kwalliya sosai wata'kila ta  tar'bar angon nata ne naga har da lalle ja da ba'ki irin wanda yake so ya yi kyau sosai a farar fatar 'kafafu da hannayenta.
Na kama hanyar d'akina jikina a galabace Minal tana take mini bayana.
Ban yi wanka ba tukkuna sai da na yi sallar magriba na fito na sami yarinyar ta bingire a gado bacci ya d'auketa. Ba ta yi wani murnar ganin uban ba kamar sauran sau daya ta je wajensa ya d'an ri'ke ta kamar yadda ya yi wa sauran ta dawo wurina. Kamar yadda twins din suka yi mini.
Sai da na shirya tukkuna na tashe ta muka fita a tare babu kowa a falon. Kai tsaye d'akin ya yaran na nufa Mairo tana ta fama da su Khali na can gefe yana rubutu a littafi.
Ta burni kuma tana gyara musu wardrobe.
Na ce." Mairo a bawa Minal abinci." Da sauri ta ce." To ta janyo hannunta zuwa ciki. Usai ta biyo bayana muka zaune kujera a tare jim kad'an itama Hassanar ta fito na daga kai na dube su a nutse tare da fad'in." Kun yi sallah ko?"
Suka daga mini kai a tare na ce." Abiñci fa?''
 Girgiza kansu suka yi. Na d'an 'bata fuska ina fad'in.'' Bebaye ne ku?''
Usai ta ce." Menene Bebaye Mama?"
Sai na fara gwada mata maganar kurame da hannuna da bakina." Aikuwa sai dariya gabad'ayansu suna kallon bakina yadda nake yi. Ni ma na kama dariyar ina fad'in." Bebaye ne masu magana da hannu da kuma gyada kai, ku kam ai kuna da baki ko?"
Da sauri  Hassana ta ce." E, wanda muke magana da shi muna cin abinci."
Na ce." K'warai kuwa daga yau idan na yi muku magana ku daina yi mini ta kurame ku bude baki ku ba ni amsa."
Suka ce "to Mama."
Na ce." Aje a ci abinci idan da aikin gida na makaranta a d'auko a yi."
Suka ce "To" a tare da sauri suka ruke hannun juna. Na sauke ajiyar zuciya tare da fad'in." Hassana duba d'akina ki d'auko mini wayata saman gado."
A tare suka nufi d'akin jim kad'an suka fito na kar'bi wayar suke wuce dakinsu.
Ina dubawa na ga miss call Hamusu ya kira ni jim kad'an da fitowa daga d'akin.
Na kira shi bugun farko ya daga muka gaisa yana fad'in." Anti Amina Gwaggo tana ta fad'a wai ba ki sanar da ita cewa Yallabai bashi da lafiya ba. Yau a gidan Hajja ta yini ta sanya ni na kaita muka je muka tarar kun tafi."
Na ce." Wallahi Hamusu ku yi mini uzuri ka bawa Gwaggo hakuri ko kuma idan ka je gidan sai ka kira ni a waya abubuwan ne sai a hankali amma ka ce mata ya ji sau'ki sosai ya warware."

Ya furta." In sha Allahu rabbi."
Muna yin sallama na hangi Hauwa na saukowa daga benansa. Na yi gaggawar janye idona daga hanyar har ta sauko ta iso tsakiyar falon na daga kaina na kalleta duk yadda take ko'karin kalato annashuwa ta ya'ba a fuskarta sai da na gane karfin hali ne kawai ta kira sunana na amsa za ta shiga d'akinta na ce." Ni kuwa akawai maganin maigidan da ake yi masa kullum da daddare Hauwa bari na d'auko miki shi zai yi miki bayani yadda ake yi masa."
Ta ce." To tare da tsayawa na tashi na shiga d'akina na d'auko mata sauran maganin da ya yi ragowa da rubutun ina fad'in zai gaya miki yadda za a yi."
Ta sake cewa ." To." Kamar mai koyon magana ta kar'ba ta shige d'akinta.
Baba Tabawa ta fito da Sultan a hannunta ya yi wayo sosai yana ta furzar da yawu alamun hak'ori na kar'be shi Ina dariya tare da cewa" Yaro ya sake wayo duka bai fi sati biyu ba rabona da ku amma kowa ya canza mini a gidan na ji dadin ganinku cikin koshin lafiya."
Ta zaune tana fad'in." Alhamdulillahi kam sai godiyar Allah."
'Daga shi sama na yi na cafe ya dinga b'angala baki yana d'igo mini da yawu a fuska. Baba na murmushi ta ce." Ai ya yi wa uwarsa yankan k'auna a gidan nan Hajiya wallahi kamar al'amara ko wanda aka rad'awa a kunne koda ta dawo ya ga 'bakuwar fuska idan ya kalleta sai ya tsalla ihu duk ya sheda fuskokinmu amma ban da tata 'kiri-'kiri ya'ki yarda ta d'auke shi, da ta tsananta a washe garin ranar da ta dawo don kuka sai da ya kusan shid'iwa ya yini yana baccin wahala daga lokacin tace kada a kara fitowa falo da shi falo. Idan kuma ana canza uwa sai ya canza. Wai ta ji haushin abinda ya yi mata."
Murmushi kawai na yi ina d'an cire hannunsa da yake janyo mini d'ankunne a takaice na ce." A hankali zai saba da ita dama ai mussaman yaro mai 'kuiya yake." Ba na so maganar ta yi tsayi a tsakaninmu don ban san abinda za ta haifar ba.
Nan falon na zauna na ci abinci muka yi hira ta yaushe gamo da Baba Tabawa wajan yara da arba'in Hauwa tun da ta shiga d'aki bata fito ba shima maigidan tunda ya sauko wajejan Isha'i ya fita bai shigo ba har na yi sallama da Baba ba shige d'aki. Isha'i na yi kawai na sanya kayan bacci na kwanta amma raina gabad'aya babu dad'i ba na son wannan matsalar ta su ta shafi lafiyarsa Malam D'aha ya jadadda mini cewa kada a tsallake rana d'aya wajan aiki da abinda ya bayar. Ban hangi wani sasanci da d'okin juna a tsakaninsu ba. Hauwa ta kar'bi maganin ne kawai domin kada ta nuna mini akwai matsala tunda abinda na karanta kenan a fuskarta amma ai ni ba yarinya ba ce tun saukowarta na karanci tsananin damuwa da tashin hankali. Yadda na yi wa Hajja alkawarin kawo zaman lafiya a tsakaninmu hakan ne ya sanya ni bata damarta a matsayinta na wadda ta yi kome gidan mijinta dole ita zata shiga turaka idan magana ta gaskiya za a yi. Na d'auki wayata domin kiransa. Ko da ta shiga bai yi jinkirin d'agawa ba.
Na ce." Allah Ya taimake zan ce dama sai da safe domin na yi ta jiran ka shigo mu yi magana shiru ragowar maganinka na wajen Malam D'aha na bawa Hauwa na ce sai ka yi mata bayanin yadda ake yi maka ko?"

Ya ce." Akan wane dalili Amina?''
Shiru na d'an yi ina mamakin maganarsa. Dalili saboda matarsa ce ya yarda ta dawo su cigaba da rayuwa an yi musu sulhu iyaye sun shiga yanzu zaman aure za mu yi babu cin amanar juna da zalintar wani.
Ya sake maimaita maganarsa da b'acin uana fad'in." Sai ki je ki kar'bo mini maganina idan ba za ki zo ki yi yadda ki ke yi kullum ba ki kawo mini na yi abina."
A dan daburce na ce." Ai ba da gangan na'ki zuwa ba sanin da na yi cewa dole ne itama a bata damarta hakkinta ne kuma..... Ya katse ni
"Ni na ce ta dawo?"
Shiru na yi ina sauraransa.  Ya cigaba da cewa." Ki je ki ce ta baki magani na ki kawo mini ina da lafiya Allah ya hore mini ba ni da nakasa a hannu zan gudanar da komai."
A tak'aice na ce." Gaskiya ba zan iya ba ai na riga na bata."
Ya datse wayar ba tare da ya sake magana ba.
Na kashe na nemi gado na kwanta ina fad'in" Ban da rigima ai da tun a can sai ka gayawa mahaifiyar taka baka amince ba, haba a yi ta abu daya sai kace 'kananun yara."
Jin yawu ya d'an ciko bakina ya sanya ni tashi na bud'e dirowa nan na sanya ledar da Hajara ta aiko mini da ita na ji dad'i sosai kuwa tun a gidan Hajja dana bud'e na gani magarya da kurna taura da aduwa har da tsamiyar biri irin kayan motsa baki na gargajiya.
Aduwa na d'iba na zauna gefan gado ina tsotsa a tsanake ina duba wayata What'sapp na shiga na ga sa'kon Nusaiba ya shigo voice note ko da na bude sai na ji muryarta har tana rawa tana gaishe tana fad'in ta zo gidan ba na nan har sau biyu zuwanta na k'arshe Hauwa ta ce kada ta 'kara zuwa domin ita najasa ce da mahaifiyarsu.
Voice na biyu kuwa kuka take yi tukuru tana fad'in. Anti Amina don Allah kada kema ki k'yamace mu don Allah kada lefin da mahaifiyarmu ta yi ya shafe mu wallahi tallahi ba mu ta'ba sanin abinda take aikatawa ba kenan, ta rasu ta dasa mana tsangwama da k'yama a wajan mutane ba mu da lefi kada ke ma ki tsane mu antina......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[5/3, 2:50 PM] +234 803 054 1544: https://chat.whatsapp.com/E8JgnaAUG13CRwJbYeXImE?mode=gi_t
 ☘

*TALLAH!*
*DA MAGANI A GONAR YARO!!*
*08089965176*
*07084653262*
*Dayawa akwai matan da suke da matsala ta lalacewar nono yamushewa da kuma fad'uwarsa. Wasu ma 'yan mata ne basu kai ga matakin aure da shayarwa ba amma sai su samu matsalar faduwar nono. To gaskiya akwai magani sai dai kawai idan ba a yi dace ba. Wasu zasuyi ta faman kashe kudi

amma buk'ata bata biya ba, wasu kuma zasuyi ta fargaba kada su je garin neman gira a rasa Ido, ma'ana su sayi abinda zai cutar dasu da kudinsu. Kuma yanzu dai tsakani da Allah rijalu sun riga sun gama nuna abinda suka fi karkata a kansa a jikin 'ya mace kirji da kuma baya. Wasu Allah ya hallice su dashi har ya yi musu yawa, wasu kuwa basu dashi kuma mai saurin zubewa ne. To mu dai duk wanda ya san maganinmu ya san ingantacce ne, kuma Yana aiki kwarai da gaske wurin dawo da daraja da martabar nono da izinin Ubangiji. Sahihin magani ne da ya samu sheda da lambar yabo, kuma Islamic ne da akayi masa hadi mai inganci domin gyara jikin mace ba ma iyakacin nono kawai ba. Babu nadama haka zalika babu dana sani da asarar dukiya wurin sayan maganinmu. In sha Allah matsalar ki zata gushe idan kin jarraba amfani dashi. Ba mu tsaya ina nan ba, muna da na gyaran hips sahihi dana k'iba idan kina fama da matsalar rama. Haka zalika muna dana tumbi, da kuma maganin sanyi mai mugun kyawun da yake kassara kowane irin sanyi na fili da boye wanda zaku hadu da maigidanki kuyi amfani tare. Akwai ingantattun supplement wad'anda basu da illa balle su cutar da GARKUWAR jiki. Sai dai su gyara su kuma tayar da komad'a ina nufin inda ya samu nakasu a jikinki. Muna sayar da sabulan gyaran jiki dilka da man gyaran gashi, muna kuma bayar da sari a fad'in najeria da nijar muna tura kayanmu kowane gari da ikon Allah.*
*Muna garin kano duk inda kake za mu aika maka da kayanmu. Domin neman karin bayani sai a yi mana magana ta Whasap ga lambobin da za a same mu a kai.*
*07084653262 ko*
*08089965176*
*SIYAN NAGARI!!!!!!*
*A JARRABA A SAMU BIYAN BUKATA DA YARDAR ALLAH*

*Gudun aure littafin kudi ne complete 2k akan telegram normal What'sapp group 1k via 0542382124.... Binta Umar gtbank*
*07084653262*
*134*
Ina tsaka da mamakin abinda Hauwa ta aikata ya shigo dakin ransa a 'bace ganin haka ya sanya ni daidaita yanayin fuskata. Fad'a ta inda yake shiga ba tanan yake fita ba duk akan na d'auki magani na bawa Hauwa kamar zai mangareni da duka. Na yi shiru kawai ina jinsa ban tanka masa ba ya gama da fad'in na tashi na je na kar'bo masa maganinsa. Nan fa d'aya na ce ba zan je ba na nemi waje na kwanta raina gabad'aya a b'ace wai shin yaushe za mu samu zaman lafiya ne a gidan nan. Ni a ganina abinda na yi shine daidai da adalci ban d'auka cewa zai zama lefi tunda ai shima yana son lafiyarsa
Me yasa ya amsawa mahaifiyarsa ya san bai shirya cigaba da zama da ita ba. Ba ni so daidai da kwayar zarra hakkinta ya kama ni. A yanayinta dai sulhu da sasanci take nema tunda har ta iya yin ado da kwalliya dominsa ta kuma bi shi dakinsa to ai sai ya yi hakuri ya yafe tunda zahiri shi ma yana yi mana lefin kuma ha'kuri yake yi da ita.

Ina kallonsa ya shiga toilet dina ya yi uzurinsa ya fito d'aure da alwala ya zauna saman dadduma ya bude Al'kur'ani mai girma yana karantawa daga tsakiya suratul-kahfi sai da ya kammala ya rufe al'kur'anin bai nade daddumar ba ya kwanta a samanta tare da takurewa kamar wani maraya.
Na tashi zaune ina duban bayansa da mamakin abinda ya yi akan ya yi wa Hauwa magana ko ya kwana d'aki daya da ita gwara ya kwanta a kasa bisa dadduma wace irin zuciya ce wannan ta riko da gaba mai tsanani.
Ina ta yi masa magana ya yi mini shiru kuma idonsa biyu tunda ina ganin haske wayarsa yana dubawa.
Na sauko daga gadon hijabina na sanya na bude d'akin na fita dole na kar'bo maganin na shafa masa tunda na lura shi akan hakan sai dai duk abinda zai faru ya faru ga lafiyarsa amma ba zai kwanar mini a d'aki ba balle ta fahimci haka ta ji haushi ko ta zarge ni.
Na bubbuga kofar d'akin nata ta zo ta bude mini ta yi sabon wanka cikin kayan bacci tana kamshi na ce." Maganin nan za ki ba ni."
Sai ta yi kasa'ke tana kallona cikin nazari na yi kasa da kaina ina jinta tana fad'in." Yanzu nan fa na gama shiri zuwa saman ya dawo ne?''
A tak'aice na ce." E, shine ya ce a bashi." Ta juya jikinta a sanyaye ta d'auko mini na kar'ba na ja mata kofar.
A zaune na same shi yana waya ya gama ya koma ya kwanta bai dube ni ba.
Na daura tare da furta." Ga maganin na kar'bo."
Ya yi mini shiru bai ce komai ba.
Shiru d'akin ya d'auka kusan minti goma sha biyar ba shi da niyyar tashi ya d'auki maganinsa ya fita.
Na ce." Ni fa wallahi ba zan yadda da wannan rayuwar ba. Ba zan ta'ba amincewa na zalinci wata ba mu yi maganar gaskiya a tsakaninmu kada ka so zuciyarka akan duk abubuwa da suka faru Hauwa matarka ce kuma 'yar uwarka ni kuma na dauketa abokiyar zamana tunda ka ce na kar'bo maka maganinka gashi ka tashi ka tafi wajenka ta sameka a can shi yafi alheri."
Uffan bai ce mini ba sai ya mika hannu ma ya d'auko fillo daya daga cikin wad'anda suke jere a saman gadona ya gyara kwanciyarsa.
raina ya b'aci sosai na kwanta jikina a sanyaye ina kallon bayansa da tarin mamakin abinda yake yi. Ni dai anan ban ga lefin da na yi ba kuma da zai tsiri jin haushina.
Damuwa ta cunkushe mini da fargaba domin yadda ya yi zuciya da kallon inda nake haka yake so ya yi wa lafiyarsa mugunta.
Kaina ya fara sarawa tsabar takaici na rintse idona domin kirkiro bacci amma nasan ba zai ta'ba zuwa ba.
Can na fara jin saukar numfashinsa alamar bacci ya d'auke shi. Na tashi zaune da sauri da mamaki da gaske yake yi
Na zuro 'kafata kasa ina le'ka fuskarsa bacci yake sosai kuma cikin kwanciyar hankali. Na tashi na je na d'auko kayan maganin na zauna kusa da shi tare da d'an bubbuga fillon da yake kwance ya bud'e Ido yana kallona da yanayin bacci. Na ce." Ka tashi na shafa maka."

Ya tashi kamar yadda na umarce shi da kansa ya cire kayan jikinsa. Ban ce komai ba na fara shafa masa yana ta bina da kallo har na gama bai yi magana ba ya mayar da rigarsa da wandonsa na ciki ya koma ya kwanta.
A haka muka kwana a d'akin kai da gindi. Sai da asuba ya fita bai kuma kula ni  ba. Na kasance cikin mamaki sosai shikkenan daga gyara kayanka Allah Ya sawwa'ke.
A haka kwana biyun da Hauwa ya kamata ta yi da shi suka shud'e a banza ba ma ya yarda ya kwanta a dakinsa balle ta biyo shi sai ya taho nawa ya kwanta kuma ba zai mini magana sai dai idan na gaji na yi masa idan na zo na shafa masa maganin sannan yake amsa mini amma bai ri'ke mini hannu ba balle ya ce zai nemi wani abu.
ranar da na kar'bi girki da yamma na shiga kicin domin hada masa fruit-salad kamar yadda ya buk'ata. Baba Tabawa da Taburni suna ta hidimar abinda za a ci daddare.
Muka gaisa kafin na ji maganar Baba tana fad'in. " Ban da abinki Taburni ai ba ita ta d'auke ki aiki ba to me zai sanya ki damu da abinda ta ce don Allah ki yi hakuri me yasa za a yi ta maimaita magana d'aya."
Na ce." Menene kuma?''
Murmushi ta yi tana fad'in." Ita da Hajiya Hauwa da alama jininsu bai hadu ba tun bayan dawowarta kafin ku dawo ke da maigidan su ka d'an yi sa'insa abin dai babu arziki da b'angaran Hajiya Hauwa kamar yadda ki ka san halinta na cin mutunci wallahi har da zagi wai zamansu ba shi da amfani mun had'u har da ni munafurcin banza.  daga lokacin ko Taburni ta gaisheta ba ta amsaw.........." To me zai sanya ni amsawa Tabawa"
Muryar Hauwa ta katse maganar Baba Tabawa gabad'aya muka juya muna kallonta. Ni mamaki ne ma ya kama ni yadda yau ta kira Tabawa kai tsaye babu ma Baba dukkaninsu dattijai ne cikinsu babu wadda ba ta haife mu ba ai rashi ba hauka ba ne don suna masu aiki  sai su zama wulakantattu."
Ta shigo kicin din sosai tana fad'in." Baba Tabawa tunda Amina ta dawo ki 'kara kuzarin gulma da munafurci yanzu don Allah ba ki ji nauyi da kunya ba da girmanki da shekarunki?
saboda ni ba ni da kudi ba na baki toshiyar hanci shiyasa ba ki d'auke ni a matsayin matar gida ba. Matsiyaciyar matar can wadda ta yi mutuwar wulakanci tun tana raye kike maula da yi mata fadanci kada ki ce na manta duk abinda zai faru ba ki ta'ba goyon bayana ba Amina da Maryam sune mutane tunda suna sinna miki. To a shirye na dawo na gaya miki kowane sakarai da sha'kiyyi zan daidaita masa zama wallahi na kuma fad'a Mairo da Taburni sai kun bar gidan nan domin duk wani abu da ya danganci matsafiyar matar can najasa ne ba za ku hana mala'ikun rahama shigo mana gida ba."
Baba Tabawa duk yadda ta kai ga daurewa sai da ta fashe da kuka ta sanya tafin hannunta ta 'kunshe bakinta hawaye share-share a kumatunta. Tunda na d'auki baiwar Allah nan aiki tsayin shekaru kusan biyar tsakanina da ita alheri ne da kyautatawa da wasa da dariya amma yau Hauwa ta dubi tsabar idonta tana kiranta da munafukai shakiyya sakarai.
Taburni ta jingina a jikin wardrobe din kicin din tare da sunkuyar  da kanta.

Bakincikin da nake ciki ya sake hauhawa ai na d'auka ta yi sanyi ta dawo ne domin ta gyara kuskuran da ta yi mu zauna lafiya ashe ba haka ba ne a zuciyarta da wani shirin ta zo.
Na dube ta sosai ina fad'in." A matsayinki na wa za ki sanya su barin gidan ko ke ce ki ka d'auke su aiki ki ke biyansu?"
Ta gyad'a kanta tana cewa." A matsayina na matar gida kamar yadda ki ke matar gida ko da bambanci ne a tsakaninmu."
Na ce." Da bambanci kwarai da gaske Hauwa Ina so na gaya miki ki gyara kalamanki akan wad'an nan dattijan Annabi Muhammadu s.a.w ya ce ka girmama furfura ko ta wacece ke yanzu don Allah ba ki ji kunyar duban tsabar idon Baba Tabawa kin gaya mata wannan maganganun ba."
Ta ta'be baki tana fad'in." Ita ba ta ji kunyar abinda take yi ba ai munafukar tsohuwa ce."
Na buga mata tsawa sosai ina fad'in." Wallahi tallahi Hauwa za mu yi ta dake gidan nan akan wad'an nan da suke tsaye na gaya miki."
Ta girgiza kanta tana fad'in.'' Na ji duka to Amina na ce ki rufe ni da duka."
Na ja tsaki kawai ban sake wata magana ba na juya bangaransu ina ba su ha'kuri zuwa lokacin itama Taburni kukan take yi tana fad'in." Shiyasa na ce fa tafiya zan yi cikin iyalina  na yi abinda na yi Hajiya Amina ba na so a kaskantani ki yi hakuri ni ba ki yi mini komai ba amma don girman Allah ki sanya a mayar da ni k'auyenmu.
Na ji 'kwalla ta ciko kwarmin idona na dubi Baba Tabawa da take goye da Sultan a bayanta yana ta bacci idonta duk ya kumbura tsabar kukan da ta jima ba ta yi irinsa ba. Na gyad'a kaina in banda rashin mutuncin Hauwa matar da ta rungumi d'anki da ki ka dangwarar ki ka tafi take yi masa wahala itace abar zagi da aibatawa. Lallai da gaskiyar Hajja Hauwa ba ta da kunya yau na sake gasgazatawa tunda ita duk girma da shekarun mutum furfurasa ba ta hana ta yi masa diban albarka.
Da kyar na iya had'a fruit-salad din ina yi ina basu baki Hauwa ba su kadai ta ci mutunci ba har da ni da maigidan gabad'aya ta tsinka. Na had'a masa abinci tsaf tunda lokacin su ma sun kammala na kai samansa na jere inda yake zama.
Na yi wanka da sallar magriba na shirya na zauna kaina ya kulle gabad'aya na rasa ta yadda za a yi na fara yi masa bayanin abin nan da yake faruwa wanda na tabbatar da cewar wani sabon tashin hankalin ne zai sake faruwa a tsakaninsu tunda haushinta yake ji dama.
Ya kira ni a waya na tashi na je na same shi ya sake sosai ya daina gabar yana ba ni labarin Bashir kanin marigayiya cewa an yanke masa hukuncin zaman gidan kaso na shekara goma sha biyar tare da horo mai tsanani babu kuma biyan tare tunda dama tsohon mai lefi ne nemansa ake yi ruwa a jallo dilan wiwi da 'kwaya ne ga 'yan sace-sace yana ta'bawa.
Jin sa kawai nake yi hankalina baya kansa amma dai na yi kokarin aro jarumta ban bari ya fahimci cewa akwai rikici ba.
Da asuba yana fita salla na sauka kasa. Kai tsaye d'akin yaran na leka tare suke da Mairo dama har ta yi musu wanka tana shiryasu da kayan makaranta. Khalil da yake ya girma shi da kansa yake shiryawa. Muka gaisa

da su na wuce wajansu Baba Tabawa na same su suna dambarwa Taburni ta had'a kan kayanta ta 'kulle a d'ankwali tamau wai tafiya za ta yi rarrashinta ya hana Baba Tabawa shiga kicin kamar dai koyaushe. Ganin da gaske take ya sanya hankalina ya tashi ba ni son rabuwa da matar gabad'aya ita kuma yadda ta yi fushi koda an bar ta tafi garin nasu ba lallai ta dawo ba.
Gabad'aya muka fito fallo na yi na yi da ita ta yi hakuri ta'ki Mairo da yaran gabad'aya duka suka fito aka yi cirko-cirko. Minal ganin Taburnin tana kuka sai itama ta fashe da kuka da kar'fi  don da alama hayaniyar da ake yi da kukan da suke yi su biyu ya tsorata kukan ta ya yi daidai da lokacin da ya shigo ya fara fadin." Lafiya a d'an ki'dime yana kallona domin neman karin bayani."
A tak'aice na ce." Taburni ce za ta tafi." Ya sunkuya ya d'auki Minal din yana rarrashinta da yanayi na damuwa ya furta.'' Taburni ke da na ce miki muna buk'atar zama tare dake yara sun yi sabo daku yanzu ki duba ki ga yadda Minal ke kuka ganin kina yi, ki yi hakuri ki zauna tare da mu duk abinda ya kamata na kulawa za a yi miki daidai gwargwado."
Ta sa gefan mayafinta tana fad'in." Dole ce ta sanya ni tafiya Alhji amma ni ma ina son zama daku."
Ya ce." To shikkenan ki gaya mini me aka yi nasan lallai ruwa baya tsami banza."
Shiru falon ya d'auka babu wanda ya yi magana. Sai da ya sake maimaita maganarsa tukkuna a sanyaye ta furta." Amaryaka da ta dawo ita ce bata buk'atar zamana a gidan."
A dan daburce ya ce." wace amaryar tawa kuma Taburni?"
Ta yi shiru tana jan hanci. Can kuma da ya gane Hauwa take nufi sai ya ja tsaki bai ce komai ba ya nufi dakinta da d'an karfi ya buga kofar d'akin ta yi magana ya ce." Bud'e malama."
Minti biyu ta bud'e ta fito da yanayi na bacci a  idonta wato duk wannan dambarwar da take faruwa a gidan ita baccinta ma take yi.
Na tausaya mata k'warai da aniya yadda ya fara yi mata tijara da kausasan kalamai wanda ke nu ni da cewa ya fi buk'atar zaman Taburni a gidan a kan zamanta idan ba za ta iya zama ba hanya a bud'e take ta 'kara gaba. Ta muzanta ainun domin ya yi bala'in tsinkata ya kuma nuna mata cewa masu aikinsa sun fiye masa ita tsit! falon ya d'auka na yi 'kasa da kaina ina jajanta mata ina kuma jin wani iri a raina yanzu me ya fi wannan takaici. Babu abinda ya fi zaman lafiya dad'i a gidan aure Hauwa da za ta d'auki shawara sam tashin hankali bai kar'be ta ba bata ta cin riba ko kad'an sai fad'uwa a gigice da borin kunya ta nufi dakinta tana kuka mai cin rai......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK 1K ON TALGRAM VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK.*
*07084653262*
*V-VIP AREWAPEN*

*135*
Ya wuce mu ya hau samansa da tsananin 'bacin rai a fuskarsa wannan ya sake nuna mini cewa dama kiris yake jira  da ita a gidan don dai haka siddan ba zai yi mata rashin mutunci ba ne sai da dalili amma yanzu da ya samu mafaka ya yi da hujja! ita aka yi wa amma ni nake jin kunya da nauyi wai hausawa suka ce sandar da ta daki uwargida da ita ake dukan amarya.
A ranar kuwa yini ya yi yana 'kuncin rai  tabbacin ta gama 'kona masa rai da kuma damuwoyin mas'aloli masu yawa a tare da shi
har ni da nake ta ko'karin sasanta al'amarin haushina yake ji. Hakan ya sanya ni rabuwa da shi na sauko na yi kwanciyata a d'akina gidan ya kasance shiru tunda ranar makaranta ce yara tun safe idan sun tafi sai yamma likis za su dawo. Da k'yar dai muka rarrashi Taburni ta janye k'udirinta ta ha'kura da tafiyar har suka shiga kicin da Baba Tabawa a tare.
Sai da daddare tukkuna wajan sha d'aya  na yi shirin kwanciya na sake komawa saman. Na same shi zaune kan dadduma yana ta karatun al'kurani abincin da na jere masa bana tsammanin ya ci. Sai da ya kammala tukkuna ya juyo yana kallona muka had'a Ido. Ya d'auke kansa yana fad'in." Zuba mini abinci kad'an amma."
Ban ce komai ba na tashi na isa wurin abincin kamar yadda ya buk'ata shinkafa ce da taliya da miyar kifi masu girma.
Ya zo ya zauna da babbar wayarsa a hannu ya d'auki flat din abincin ya tallafe a hannunsa kamar yadda yake yi wasu lukutan ya fara da Bismillah sai da ya kusa cinyewa ya ajiye flat din ban ce komai na sanya a hannu cikin abincin na fara gyara masa kifin da bai ci ba duk da manya ne marasa k'aya amma dai ba a rasata ko yaya ne. Ya ci kifin sosai don da alama ya fi bukatarsa a kan nama idan shine ba zai yi masa irin wannan cin ba.
Na tsinci maganarsa yana fad'in.'' Amina Hauwa tana ganin tana da wani matsayi mai girma a gidan nan ko?'
Na yi shiru ban ce komai ba domin ni gabad'aya ma al'amarinsu ya ishe ni. Ya cigaba da cewa." Yara da suka ratsa tsakani na da ita ne kadai suke ri'ke da ita amma wallahi zan fad'a miki gaskiya ba ni son na bud'e idona na ganta cikin gidan nan nawa sai dole akan wad'an nan dabi'un da ta fara za ta sake fita domin ba ni had'a kowa da masu aikin nan mussaman Mairo da Taburni ina ganin 'kima da mutuncinsu duk wanda zai tsaya tsayin daka akan abinka ai masoyi ne."
Na ce." K'warai kuwa amma ita Baba Tabawa saboda ni na kawo ta bata da muhimmanci da zamanta da babu a gidan duk daya ne a wajenka ko."
Ya dube ni yana fad'in." Ban ce ba Amina ai ban ware ba har da ita na ke nufi."
Ya mutsa fuskata na yi ban ce komai ba. Ya gama cikin kifin na tattara kayan abincin na sauka da su k'asa na wanko hannuna tsaf na sake komawa saman na same shi zaune a wajen bai tashi ba.
Na dube shi sosai ina fad'in" Yau bacci ne a idona sosai za a shafa maganin yanzu ko sai na kwanta."
Ya lumshe idonsa tare da bud'e su a kaina yana fad'in.'' E, amma mu dan yi wani abu kafin wannan ."

Na gane abinda yake nufi na dan 'bata fuskata kadan ban shirya kwanan tashin hankali da damuwa da kewa ba domin dai tsakani da Allah duk yadda yake ko'karin ganin ya samar mini da nutsuwa ba ta gamsar da ni ha'kuri nake yi kawai sai nake ganin idan bai ta'ba ni ya tsokano ni ba hankalina zai fi kwanciya.
Cikin rarrashi da kwantar da kai har sai da ya ba ni tausayi ya samu ya hillace ni a daran muka yi soyayya sosai ya samu biyan buk'atarta kwarai daga nawa bangaran kuwa abin sai a hankali har sai da na yi kukan b'akinciki a toilet anya rayuwa za ta tafi a haka kuwa gashi maganin da malamin nan ya bayar ya kusa k'arewa saura na kwana biyu kacal babu wani canji.

Sai da na yi kwana uku ban sanya Hauwa a idona ba tana d'aki a kwance na fi tunanin sai ta ji sahu ya d'auke take fitowa ta yi abinda za ta yi a kicin din ta dibi abinda take so ta koma. Ai dole kunya ma yanzu ta fara har in dai ba za ta daidaita tunaninta ba ta zauna lafiya da kowa.

Kuma har yanzu duk ranar girkinta wajena yake kwana idan na shafa masa magani sai ya yi kwanciyarsa idan ina yi masa nasiha da rarrashi kamar da kurma nake magana sai ya juya mini baya kawai sai na zubawa sarautar Allah ido. Tunda duk abinda ya kamata na yi na yi wannan shine alkawarin dana daukawarwa mahaifiyarsa.
Yau ne zai je bunkure kamar yadda muka gama maganar jiya magungunansa sun kare malamin ya ce ya je ya same shi gobe Kuma Hajiya Maryam za ta cika kwana arba'in da rasuwa mun yi waya da Nusaiba kan cewa tana so ta zo gidan su yi aikin funkaso da fanke duk na gaya masa bai ce kada ta zo ba.
Da assubaha ya fita daga d'akina don haka gari yana d'an yi haske kad'an na bi shi nasan ya dawo daga massalaci yana shirin tafiya tunda ya ce su biyu kadai za su tafi da Sukairaju kuma ta jirgi ce yau din yake so su je su dawo idan lokaci ya bada damar hakan.
Na ji maganganunsu tun kafin na murda kofar d'akin sai na yi saurin cire hannuna daga handline din.  Ina jinta cikin kuka mai ta'ba zuciya da 'kas'kantar da kanta tana cewa." Hajja cewa ta yi na zo na cigaba da kula da yarana to me zai sanya ka had'a kai da matarka har da masu aiki ku dasa musu tsoro da k'yamata. Tun da kuka dawo nake bin ka ina baka ha'kuri don girman Allah ka yafe mini na yi kuskure ba zan kara ba amma ka daina tozarta ni da nuna mini iyakata a gaban Amina, ban cancanci wannan wulakancin daga wurinka ba tun da ka aure ni kake nuna fifiko akan matayenka Maryam da Amina idan ka amince da cewa Hajiya Maryam tana yi maka asiri akan ta samu soyayya da d'aukaka a wajenka to wallahi ya zama dole ka amince da cewa Amina ma tana yi maka asiri domin ko makaho ne ya duba ya san kana yi mata makauniyar soyayya irin wadda hankali ba zai d'auka ba sai an bi mutum ta k'arkashin kasa. Ni da kai iyayenmu daya cikinsu daya ba zan ta'ba cutar da kai ba domin kai dan uwana ne mijina kuma uban yarana b'acin rai ne kawai ya sanya ni ajiye yaron nan na tafi gidanmu saboda jingine ni da ka yi baka kula ni  naga ai babu amfanin zamana a gidan. Amma don girman Allah ka yi hakuri ka yafe

mini kuma yarana su dawo hannuna don gaskiya ban yarda da tarbiyar da ake ba su ba.
Na ji shi yana fad'in." Ke a ganinki tarbiya ce dake Hauwa. Ko kin d'auka wata fitacciya ce ke a zuciyata ne? ki kiyaye ni wallahi idan za ki yi sakarcinki kada na kiara jin kin ambaci sunan Amina. Idan kin danganta Maryam dake bai dame ni ba, amma Amina ba ta da zunubi na itace matar da take rufa mini asiri cikin kowane yanayi. Babu ke a cikin zuciyata Hauwa kuma ba na tsammanin za ki ta'ba samun gurbi a cikinta. Kin yi abinda ya kamata ace hukunciki ya fi haka muni amma arzikin yara da zumunci ya hana hakan don haka ni ban ri'ke ki ba idan kin ga ba za ki iya zama ba ki tafi kawai hankalina ma zai fi kwanciya yara kuwa ai za su rayu tunda ba ke ce mai rayawa ba."
Tana kuka take fad'in." Idan kuwa aka yi mini haka ba a yi min adalci ba anzalince ni kuma wallahi sai Allah Ya
saka mini."

gudun aure littafin kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina bam

Ya furta." Ki ka zalinci kanki dai Hajiya hakkin Sultan kadai ba zai bari ki samu sau'kin zuciya ba, ni dai ba zan sake rayuwar aure dake ba balle ki samu ciki ki haihu ki ajiye mini yaro ki tafi. Ki zauna dai a gida gashinan babu wannan alak'ar a tsakanina dake yanzu."
Da tashin hankali mai tsanani na ji tana fad'in ." Wallahi abinda ba zai yiwu ba kenan ai zalinci ne wannan kuma ni mutum ce ina da bukata a koyaushe me yasa za ka yi mini haka ina kallo kana mu'amula da matarka ni kuma ka ce ba za ka yi da ni ba, zan gayawa Hajja domin wannan abin ya ishe ni ko da can ma ai sai na nema kake kula ni ba ka zuwa wajena don ra'ayin kanka sai na yi ta bin ka, da haka duka muka tara wannan yaran da ake yi mini gadara a kansu, wallahi ba zan iya jurar wannan wulakancin ba."
Ya ce." Kada Allah Ya sa ki jure din ko ni ne na ce miki ki dawo da zan damu kaina tafiyarki kwanciyar hankali da nutsuwa ta haifar mini a gidana ai ke ce ba ki sani ba."
Da gunjin kuka da jan hanci na ji tana cewa." Shikkenan na ji to ka rubuta takardata ka ba ni zan tafi har abada kuma ba zan sake sha'awar sake zama da kai ba ai ko Allah ma ana yi masa lefi ya yafe."
Hankalinsa a kwance ya furta." Idan na sake sakin ki a yanzu na zama sakarai kenan. Ki zauna dai ki ga ikon Allah aure ma zan k'ara bayan Aminata na yi rayuwata da iyalina cikin hayyaci da samun nutsuwa. Na fi ki mugunta da d'anyan kai Hauwa ko kin d'auka cewa ke kadai ce mara ji ne?"
Ta yi shiru tana jan hanci.
A hankali na ri'ke karfen baranda gabana na dokawa na fara sauka maganarsa na yi mini kud'a a tsakiyar kunnena 'aure ma zan k'ara na yi rayuwa da iyalina.' Shin da gaske ne ko kuma barazana ce kawai yake yi mata domin ya gigitata. Zuciyata take rada mini aure a ina mutumin da ba shi da lafiya babu karfi irin na jarumar maza. Daya sashen ta na ce mini duk

da haka ai akwai da dama mazan da ba su gama kawar da matsalar iyalinsu ba amma suke rakito auran.
Na zauna jigum da mamaki a cikin raina. A
amma dai bari mu gani lokaci shi zai nuna.
Ina kwance ya shigo ya shirya tsaf cikin manyan kaya ya kuma yi kyau ainun kamshinsa yana ta sirnanowa hancina muka gaisa dama na ware kayan da nake so ya tafi da su turmin atamafa ne biyu da mayafi sai takalma guda biyu duka sawa ta daya sun yi mini tsayi duk da nake gajeriya ba kasafai nake son takalmi mai tudu ba na ce masa sa'kon Hajara ne a ce mata na gode da abin arzi'ki.
tare muka fito falon shiru yaran ba su fito ba suna ciki ana shirin skull.
Ya d'an tsaya yana kallona kafin ya janyo ni ya matse tsam a kirjinsa na dan wani lokaci ya cika ni tare da juyawa da sauri ya kama hanyar fita na sauke ajiyar zuciya a kasalance na ce." A gaishe mini da Hajja sosai Allah Ya tsare." Ya amsa da "Amin kafin ya fita.
Ina juyawa da zummar komawa d'aki na ga Hauwa a tsaye a bakin kofar dakinta. Na yi kasa da kaina ba tare da na sake kallonta ba na wuce sai ta zo ta sha gabana muka dubi juna.
Murya a dashe alamun ta ci kuka ta k'oshi ta furta." Kin yi nasara a kan Hajiya Maryam Amina kin dawo kaina ko, kin rantse dai sai kin rayu ke kadai a gidan nan to bari ki ji abinda ba ki sani ba ko kin yi nasarar fitar da ni daga cikin yarana tana jika domin da bakinsa ya fadi cewa aure yake nema kuma in sha Allahu rabbi duk wadda za ta shigo itace za ta karya alkadarinki."
Na jima ina kallonta sosai ina kuma tunano irin zaman da muka yi da ita a baya a lokacin da ta dinga nuna mini k'auna da kara akan rigingimun da suka dinga faruwa. Har ga Allah a lokacin na ya ba da kokarinta kwarai duk da ina cikin kokwanto tunda bata buda mini zuciyarta na ga zahiri ba a aikace take yi komai da ita muka dinga ya'ki a gidan nan akan Maryam da d'anta Salim ta yi mini mubaya'a domin jajanta mini abubuwan da suke faruwa. Wannan shine dalilin da ya sanya ni nake iyakacin bakin kokarina akan lamarinta an ce duk dan halak baya manta alheri a lokacin tare muka dinga fafutukar kwatar 'yancinmu a wajan gidan
Amma cikin wad'an nan kwanakin gabad'aya kaina ya kulle a kanta na rasa da wane ma'auni zan auna al'amuranta. Hakan ya nuna mini cewa dama can tana ya'ki ne a kan kanta domin ta cimma wata manufa tata. Lallai Ubangiji baya bacci kuma yana tare da mai gaskiya.
Na dube ta sosai ina fad'in." In ban da abinki Hauwa ai ni ban isa na kore ki a gidan nan ba. Ni a suwa kuma ke da ki ka d'auki tudu biyu ai ke ya kamata a ce kin yi nasara a kaina na fita na bar miki gidan. Amma bari ji ki sirrin nasarata a kanki da zuciya daya nake zaune dake kuma ban zalinceki ba, ban nemi kai ki kasa ta k'arkashin 'kasa ba sai ko'karin ma ganin mijinki ya duba halin da ki ke ciki na kad'aici da damuwa. Amma idan kina ganin za ki iya had'a kafadarki da tawa to bisimillah sai mu fara buga wasan daga yau ni dake. Amarya kuma ai a shirye nake da zuwanta ko kin d'auka ina tsoro ne? ta shigo mu zauna namiji mijin mace hud'u ne a ciki kuwa dole daya ta yi

zarra nasan kuma na cinye wasan tuntuni. Don haka tunda kin  biyo ta wannan hanyar mu zuba ni dake shege ka fasa.''
Na wuce a gaggauce na shige d'akina domin bana buk'atar sake jin komai daga bakinta.  Tunda ta ce za ta iya to mu zuba daga yau na daina d'aga mata 'kafa wallahi........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*V-VIP AREWAPEN*

*136*
Zama na yi gefan gado tare da d'umbun mamaki da al'ajabi wai yau Hauwa ce take jingina mutuwar Hajiya Maryam da ni saboda tsananin kishina da yake damunta. Kafin kowa ya san da cewa Maryam mashirika ce ita ta fara fad'in haka a bakinta na ji har nake nuna mata kuskuranta akan tabbatar da abinda ba ta gani da idonta ba. Yanzu da rasuwarta ta tona duka ayyukanta na sa'bon Allah kowa ya sheda hakan amma a yau saboda sharri da k'iyayya tana alak'anta mutuwarta da ni. Wani irin sanyi (d'ari) ya mamaye ni a take a lokacin tsabar k'aduwa da mamaki da kuma tsoron duniya. Ni dai duk yadda na kai ga kishi da nuna k'iyayyata akan kishiya ba zan iya neman hanyar da zan halakar da ita ba kamar dai yadda Maryam ta yi ba kuma zan 'kir'kiri karya ko da sharri na ya'ba mata ba. Ina da kishi sosai mussaman akan abinda nake so amma a duk lokacin da ya taso mini nakan iya sarrafa kaina zuciyata bata ta'ba kissima mini na bi wata hanyar domin cutar da kowa ba.
Zazzabi ne mai zafi ya rufe ni da ciwon kai abubuwa da yawa sun yi mini dabaibayi haka na yi wani irin bacci mara dad'i da mafarkai irin na mai mashashshara. Biyu da minti ashirin na tashi kaina ya tsananta da ciwo na daddafa na shiga toilet alwala na yi na fito na yi salla kafin na fita falon. Shiru na d'an harari kofar d'akinta a garkame kamar koyaushe tsaki na yi na wuce dakin su Baba Tabawa nan na tarar da Nusaiba ashe tun d'azu ta zo tana cikinsu suna ta hira muka gaisa sosai na tambayeta yara tace mini suna can gidan kakarsu da ta haifi Babansu. Kamar wancan lokacin ranar addu'ar uku yau ma da shirin kwana ta zo. Na ce hakan ya yi ka fi na dubi Baba Tabawa da take ta fama da Sultan yana ta rigima ta ce tana tsammanin zazza'bi ne a jikinsa don ya yi zafi. Na shiga d'akin sosai na sunkuya na ta'ba wuyansa rau zazza'bi yake da gaske kamar ni dole ne kam Dr Sailuba ta zo gidan nan ta duba mu.
Goya shi ta yi tana jijjigashi har ya yi bacci muka fito falon ni da ita ta shiga kicin ni kuma na zauna saman kujera cikin nauyin kai da bugawa.
Abiñci ta kawo mini alkubus suka yi da rana da miyar agushi ya yi mini dadi sosai na ci hud'u nasha ruwa na sake komawa d'aki na kwanta ashe tana hankalce da ni ta biyo ni dakin tana fad'in.'' Hajiya ba kya jin dadi ne tunda ki ka fito na karanci yanayinki."
Na ce." Wallahi zazzabi ni ma nake yi Baba har ma da ciwon kai."

Ta dinga yi mini sannu cikin damuwa. Na daure na tashi zaune tare da d'aukar wayata na lalubi number Dr Sailuba bugun farko ta daga muka gaisa na ce mata idan babu damuwa ko za ki zo gida ki duba ni da yaron nan Sultan nasan yau babu aiki gashi weakened muke babu matsala ko."
Ta ce." Babu komai zan shigo bayan la'asar maigidan ma baya gari ai."
A tak'aice na ce." Na gode sosai." Na kashe wayar na ajiye Baba Tabawa ta ce." Ko da akwai abinda ki ke buk'ata na game da abinci tun da naga baki ciki alkubus din nan da yawa ba."
Na ce." Da daddare ku yi mana towo a yi kuka maigidan ita yake so amma a yi mini miyata daban ta d'an yi yaji."
Ta ce." An gama in sha Allahu ta juya ta fita da sauri.''
Ledar kayan motsa bakin da Hajara ta ba ni na d'auko na tsinci tsamiyar biri na sanya a bakina saboda galmi-galmi nake jinsa na sake kwanciya da wayata a hannu. Na rasa wanda zan kira na gayawa tsakanin anti Yagana da Sahura abinda yake damuna a game da abinda Hauwa ta ce mini d'azu abin ya tsaya mini a raina. Anti Yagana na kira muka gaisa jin maganata da kasala ya sanya ta  fara jero mini tambayoyi na ce."lafiyata lau amma ina zargin ciki ne da ni.'
Ta ce." Ba ki na zargi ba kin tabbatar kuma kin gayawa mai shi ko?"
Yar dariya na yi domin nasan dalilin da ya sanyata ta fad'i haka tunda artabun da aka sha a baya na ce.'' Na tabbatar gaskiya shi din ne smma yanayi bai barni na sanar masa ba amma zan gaya masa yau idan ya dawo ya je bunkure wajan Malam D'aha."
Babu tsammanin kawai na ji ta rufe ni da fad'a. Sai da na bari ta gama na ce." Lokacin da na samu cikin nan fa yana kwance anti Yagana bai ma san a inda yake ba yanzu ne ya dan fara dawowa hayyacinsa babu abinda zai faru in sha Allahu."
Ta sauke ajiyar zuciya kad'an tana fad'in.'' Duk da haka dai Amina tunda kin san halin mijinki da zargi mussaman idan kin samu ciki kamata ya yi ace yanzu ya sani tunda ai ya jima da dawowa nutsuwa ba ki da wata hujja anan."
Na ce." Ki yi hakuri zan gaya masa in sha Allahu anti Yagana ni akwai dalilin da ya sanya ma na kira ki yanzu."
Ta ce." Menene kuma?''
Hanci na dan ja a sanyaye na furta." Hauwa ce take jingina rasuwar Hajiya Maryam da ni." Duk na kwashe sa'insar da muka yi da ita na gaya mata .
Ta ja tsaki tana fad'in." Ta dawo ashe?''
Na ce.''kwarai ta dawo amma ta ki yadda mu zauna lafiya fitinar yau daban ta gobe ma daban tana daga mini hankali wallahi domin ni yanzu anti Yagana babu abinda na fi buk'ata face zaman lafiya duniyar nan tsoro take ba ni."
Ta furta." Kin ga Amina idan za ki kwantar da hankalinki ki kwantar ina abin yake me yasa Hauwa zata razanaki har ki dinga jin fargaba a kanta. Ban yarda ki zalinceta ta kowace siga ba amma ki daina raga mata balle ta hangi lagonki ta raina ki tunda ita Yar iska ce mara mutunci to sai kema ki sanya rigar rashin mutuncin ku buga aga wanda zai ci riba ina dalilin wannan masifar."

Na ce." Anti Yagana ai na riga na yi wa Hajja alkawari ba na so na biye mata wata matsalar ta faru wadda Hajja za ta ji haka kawai dattijiwar take ba ni tausayi wallahi a ganina idan nima na biyewa Hauwa kin ga mun zama sakarkaru gabad'aya kuma maigidan ba zai samu nutsuwa ba.''
Ta ce." Ai ba cewa na yi ki biye mata ba Amina ki fita daga harkarta ki daina raga mata ko ki nuna mata kina son zaman lafiya da ita. Kuma ki yi duk yadda za ki yi wajan ganin kin sake samun gurbi a zuciyar mijinki abinda nake nufi kenan."
Na ce." Ni ma shawarar dana yanke kenan wallahi."
Ta furta." Dada kuwa ba ta da lafiya sosai Amina har sai da ta kwanta a asibiti kwananta biyu  jiya aka sallamota."
Da damuwa mai yawa na furta." Mai yake damunta ne?"
Ta ce." Lalura ce kawai irin ta girma da shekarun yau ta ce kafafunta na ciwo gobe ta ce bayanta ya 'kage abinda dai ya tsananta a ciwon har ta kwanta a asibiti ciwon wuya da ta yi eanda ta kai ta kawo ma ba ta iya motsa wuyan ya 'kage amma yanzu alhamdulillahi da sauki."
Cike da tausayinta na ce.'" Allah Ya sawwa'ke idan ya dawo zan gaya masa wata'kila mu zo dubata. Anti Yagana ina labarin Ya falmata ne ko a Whasap na jima ban gan ta ba kuma mun jima ba mu yi waya ba.
Ta ce." Ai Ya falmata tana saudia neman kud'i Baban Saude ya shige mata gaba wajan mahukunta sai da Alhaji Bana ya sake ta."
Na ce.'' To kin ga wannan shine adalci ai ko banza ana samun jajurtatun iyaye a family kamar irinsu Baban Saude da yawa mazan da suke zalintar matayensu za su shiga hankalinsu.
Abinda ya faru shine kowa ya san da cewar Ya falmata macace mai zafin nema domin ni kaina itace madubina kuma sai da na takata tukkuna na tashi. Harkokinta sun bukasa sosai a lokacin da muka had'a karfi da k'arfe domin gina gobenmu muka tashi a tare. Tun bayan da na yi auran nan sai kasuwancin da muka yi da ita ya raunana dalili duka ta nuna mini hanyoyin yadda zan dogara da kaina da kuma yadda kayana za su cigaba da zaga 'kasashen waje irinsu sinigal nijar mali kamaru da chadi har ma da saudiya dama kusan sune suke sayan kayanmu a lokacin da muke fafutar ganin mun tashi manyan matan abuja ma suna saye amma duka ta hanyarta tunda ni ce mai aikin dinkawa na yi mata odarsu zuwa maiduguri ta rarraba a sassasa daban-daban.
Ta cigaba da kujiba-kujibarta ni ma na cigaba da yin tawa har Allah ya sanya ta bude katafaran shago ta zuba iyayen kekunan d'inki manyan kai da k'ananu ya yara suna aiki. Shekara daya ta sake bude wani a takaice dai sai da shagunanta na d'inki suka kai biyar kuma shago bai wai karami ba wanda yake iya cin sama da keken d'inki goma sha biyu.
Mijinta Alhaji Bana shine silar karyata domin had'a ba ki ya yi wasu daga cikin yaranta suka dinga kwashe mata kaya cikin dare suna fita da su a baggo. Idan suka sayar su raba kudin kashi uku shi ya d'auki kashi biyu yaran su d'auki kashi daya. Wataran rigima ta shiga tsakanin yaran nata da suke aikata mata haka har da makami abinda ya assasa musu zuwa gaban hukuma kenan daga nan sai suka fara tonawa junansu asiri dama kuma gefe

guda ta sanya Malamai ana ta yi mata ro'kon Allah itama ta tsananta da addu'a. Suka fadi mijinta ne me sanya su da ya ji duka da matsa ya tabbatar da sanya hannunsa wanda da da farko ya fara gardama da jayayya yana fad'in yaushe zai kai matarsa k'asa uwar yaransu har biyu. Daga lokacin ne ta yi tsalle ta dire ta ce sai ya saketa har suka shiga kotu alkali ya yanke musu hukunci daidai da abinda suka aikata ya kuma tilastashi sakinta tunda gaskiya ba namijin da kowace mace za ta yi sha'awar zama da shi ba ne.
Anti Yagana ta cigaba da cewa." Ai tana fita idda ta lallaba Dada ta tafi makka wata shida fa yanzu tun bikin Fadila
Na ce." Allah sarki Ya falmata zuciyarta a tsaye take irin ta Baban Saude ba ta son zama koyaushe tunaninta ya za a yi ta juya biyar ta koma goma. Amma ni da ta yi shawara da ni zan ce mata ta yi zamanta anan ta cigaba da sana'arta kamar zai fi alheri."
Ta ce." To ta dai ce shekara uku kacal za ta yi ta dawo sai dai mu yi mata fatan alheri kawai."
Na ce." Ubangiji Allah Ya taimake mu bakidaya anti Yagana ke kuma me ki ke sayarwa?" Na tambayeta cikin sigar tsokana."
Ta ce." Babu komai hankalinta a kwance har sai da na yi dariya na furta.'' Babansu Fadila ne ya tsaya miki anti Yagana shiyasa kike wanke goma ki tsoma biyar ba ki da matsala."
Ta ja tsaki tana fad'in." Amina ai sai mutum ma ya rasa wace sana'ar zai yi wallahi maza daga waje duk sun k'wace mana abin yi."

Na kudi ne littafin don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na ce." Anti Yagana ba ni so ki kasance daya daga cikin matan nan da barmani coge take yi wa wa'ka (Sakarai baki da wayo) na yi dariya ina fad'in." Ki yi nazarin abinda za ki sayar na baki jari don Allah."
A tak'aice ta furta."Aikuwa na gode sosai ai ba ki ga yadda Fadila take cinikin ruwan sanyi ba cikin nan da take d'auke da shi ya hanata fara zuwa koyan d'inki don har mijin nata ya sayo mata form na makarantar."
Na ce." Ai ni ya burge ni sosai da ya ke so ta yi Sana'a dalili kuwa rayuwa juyawa take yi ga kuma yadda duniyar ta zama komai ya yi tsada tunda karamin ma'aikaci ne za su taimake ki kan su anan gaba"
Ta ce." K'warai kuwa hakane ni ma in sha Allahu zan yi nazarin abinda zan sayar idan na yanke shawara zan sanar da ke."
Da jin dad'i sosai na furta.'' Yawwa anti Yaganata ko ke fa" Dariya ta yi kawai muka yi sallama cike da barkwanci da k'aunar juna irin ta jini.
Wayar mu da anti Yagana ta kara mini karsashi da kuzari na tashi na je na dauro alwalar la'asar ganin uku da rabi har da minti biyar jim kad'an bayan idar da sallata Dr Sailuba ta kira ni ta iso tana falo na ce mata ta shigo d'aki ta same ni mun saba sosai da ita tuntuni.
Ta shigo kamar yadda na buk'ata ta zauna can kujerar dake gefe a d'akin. Na tashi na same ta muka gaisa cikin kulawa na ji dad'i kuwa da ta zo da abin gwajin bf ta yi mini jinina normal bayan ta gama kai tsaye ta tambaye ni

ina da ciki na ce mata eh. Cikin raina ina tunanin fa ranar da Hajiya Maryam ta rasu na same shi tunda mun yi kwanciyar aure a daran ranar idan kuwa hasashena daidai ne bai fi kwana arba'in ba tunda itama gobe za ta cika arba'in da rasuwa.
Bayan magriba ta aiko mana da magunguñana kamar yadda ta fad'a mini kafin ta tafi muka sake yin waya tana yi mini bayanin yadda zan yi amfani da nawa maganin da kuma bayanin na Sultan tunda shi ma ta duba shi kafin ta tafi zazza'bin hak'ori ne yake damunsa magunguña ta had'a masa masu kyau tana fad'in daga zarar an bashi maganin zazzabin zai sauka don haka muka yin sallama a wayar na tashi na fita da ledar maganin nasa hannuna.
Suna kicin ba su fito ba tunda na duba d'akin babu kowa har ita Nusaiban na same a kacame suna ta aikin kwa'ba fulawa har da Mairo dama yaran gabad'aya ganin Nusaiba ya sanyasu zuwa wajenta tunda akwai sabo kuma yadda take hira da yaran ya tabbatar mini da cewa ko a can baya da suke tare da mahaifiyarta bata tsangwame su ba hakan ya nuna sun yi sabo domin da babu kulawa da ja a jiki nasan babu yadda za a yi su je wajenta za su guje ta ne da kallon rashin sani kamar yadda suke yi wa Hauwa.
Da yake kicin ne mai girma mai d'auke da na'urorin sarrafe-sarrafe hakan bai sanya sun takura ba.
Baba Tabawa da Taburni suna ta aikin towon dare kamar yadda na umarta. Mairo da Nusaiba suna kwa'be-kwaben fulawa.
Na saki fuskata sosai Ina kallonsu suna cikin nishadi lallai d'an adam rahama ne a ko'ina sai na rasa ma gaisuwar wanda zan amsa manyan na yi haka zalika ma yaran na yi na bi duka na amsa ina fad'in." Nusaiba wannan funkason zai yi dad'i har miyau na ya tsinke."
Ta kuwa sanya dariya tana fad'in." Kai anti."
Na dubi Baba Tabawa ina fad'in. " Ga maganin Sultan Dr Sailuba ta aiko da shi a bashi abincinsa sai ba shi yanzu."
Rufe bakina ke wuya Hauwa ta shigo kicin din ta fara bin ko'ina da kallo babu wanda ya yi yun'kurin gaisheta Baba Tabawa ta zo zata kar'bi maganin tana fad'in." Jikin nasa da zafi har yanzu." Ta juya da sauri tana fad'in ko dai bari na fara dama masa kamun nasa. Da yake kamu ake yi masa na nikakkiyar gyad'a ya fi son sa akan duk sauran abubuwan da ake bashi kuma shine yake kara masa kuzari da lafiya babu kuma rama a tare da shi.
Na ji maganarta a cushe tana fad'in." Ba shi da lafiya ne?''
Ba tare da na dube ta ba na ce." Eh.'' A takaice na mi'kawa Baba Tabawa ledar magungan kafin ta kar'ba sai ta yi gaggawar warce ledar daga hannuna. Duka muka bi ta da kallo da mamaki.
Ta fito da magunguñan tana duba su. Na zura mata ido da tsananin takaicinta kamar na mangareta haka nake ji a raina wai ita likita amma mara tunani da kangado .
Ta gama duba magunguñan tsaf ta miko mini na kar'ba ina girgiza kaina duk abinda zan yi a yanzu wallahi ba don ita nake yi ba. Baba Tabawa ta kar'bi maganin daga hannuna. Hauwan ta dube ta tana fad'in." Ba ni shi na duba shi."

Sai ta dan dube ni a tsorace wata'kila tana fargabar ta bata shi ya bude ido ya ga fuskarta tunda ta gaya mini ya ta'ba shid'ewa a kwanakin baya.
Na daga mata kai alamar ta kwanto shi daga bayanta ta bata shi kamar yadda ta buk'ata.
Na ji tsakinta tana fad'in." Sai kin nemi izininta za ki ba ni d'ana na gani Baba Tabawa ko kin manta ni ce na haife shi ne ikon Allah sai kallo ni Hauwa"
Babu wanda ya tanka mata Baba Tabawa ta kwanto yaron daga baya wanda ya yi daidai da lokacin da ya bude ido ya fara kusurkusur sai kuma ya sa kuka. Nasa hannuna a wuyansa da zafi.
Itama ta mika hannunta domin kar'barsa kukansa ya tsananta kuwa ta rike shi yana fizga irin ta yara yana mika hannu domin komawa wajan Baba Tabawa. Kukan da yake yi ya tsorata ni sosai ita kuma ta'ki ba bawa Baban shi gashi dai ta fahimci so yake ya koma hannunta. 'Dif!! kamar an yi ruwa an d'auke ya yi shiru jikinsa ya shika lakaf! Idanunsa suka kakkafe. Suma ya yi.... Ta gigice ainun da sai ta fashe da kuka tana kallonmu na yi gaggawar kar'bar shi daga hannunta muka yi tiri-tiri a kicin din har muna bangazar juna ni da ita Baba Tabawa kuwa tuni ta fara hawaye tana fad'in.'' Suma ya yi.
Kafin mu yi wani yun'kurin Taburni ta nufi friji ruwa mai sanyi gaske ta d'auko ta gumtsa a bakinta ta fesa masa da karfin a gaske a fuskarsa ya saki nishi! Numfashinsa ya fara hawa da sauka. Ya motsa kafafunsa. Muka fita daga kicin din a gaggauce ni da su gabad'aya rasa inda zan nufa na yi da yaron a hannuna d'akinsu Baba Tabawa na nufa hankalina a tashe yaron nan ya mutu ko ya samu wata matsalar mun shiga uku a gidan nan gabad'aya..... Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*

*137*

"Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! wannan kalmar ita na dinga nanatawa a cikin raina ina zaune  gefan gadon da Baba Tabawa take kwanciya da yaron hannuna. Duka sun yi cirko-cirko a kaina yayin da ita Hauwan take bakin kofar d'akin a tsaye ta gagara shigowa amma kallo daya za ka yi mata ka tabbatar da cewa a cikin tashin hankali take.
Numfashinsa yana ta hawa da sauka kafin a hankali ya bud'e idonsa yana juya kansa ya ga Baba Tabawa sai ya fara mik'a mata hannu alamar ta d'auke shi. Wata nannauyar ajiyar zuciya na sauke cikin raina ina tasbihi da godiyar Allah.
Ta kar'be shi a gaggauce ta sanya shi a kafadarta tana dan jijjigashi sai lokacin hankalin kowa ya kwanta ganin yadda yanayin yaron ya daidaita na juya babu Hauwa babu dalilinta dama kuma ba ta iya shigowa ba a bakin kofar d'akin ta tsaya.
Minal ta je tana jan zanin baba Tabawa tana fad'in." Mutawa ya yi Sultan din shikkenan ya mutu ko?"

Da sauri na janyota ina girgiza mata kaina alamar a a gabad'aya yaran duk sun yi tsuru-tsuru ganin yadda muka ki'dime don shi Khalil har da yin kuka kuma bai biyo mu d'akin ba.
Na ce Baba Tabawa ta zauna dashi a d'akin ta bashi abincinsa gabad'aya muka fita. Smma ko da na koma dakina kasa zama na yi minti goma a tsakani na sake fitowa Hauwa na samu a tsaye a jikin kujera ita kad'ai don duk sun koma kicin din domin cigaba da ayyukan da suke yi. Muka dubi juna na wuce ta ban ce komai ba na ji ta kira sunana cikin damuwa na juya amma ban amsa ba ta zo ta tsaya daf da ni tana fad'in" Don Allah Amina kada ki gayawa maigidan ina neman wannan alfarma a wajenki."
Na zura mata ido cikin nazartar maganarta ashe mara kunyar 'karya ce. Na ce." To akan me zan gaya masa Hauwa da dai Allah Ya d'auki rayuwarsa ne wannan zama dole ya san dalili yanzu kam tunda Allah Ya sa ya dawo hayyacinsa sai ayi ko'karin kiyaye gaba."
Ta gyad'a kanta tana fad'in na gode. Ban saurareta ba na shige dakinsu Baba Tabawa tana ta kici-kicin bashi kamun data dama masa yana cinyarta a zaune yana kamo hannunta. Na sake sauke ajiyar zuciya ta jin dadi ganinsa kalau  har ma yana d'an wasansa. Na zauna har sai da ta gama bashi  ta gyara masa jikinsa da bakinsa tukkuna na bude maganin na fara nuna mata yadda za ta bashi koda ta kammala sai ta sanya shi a kafad'a ya yi gyatsa sannan ta d'auki towel dinsa ta goya shi. Yana ta gwalantu irin na yara.
Fitowata daga d'akin ya yi daidai da lokacin  shigowarsa. Dama ya ce da wahala ya kwana. Na yi kokari sosai wajan daidaita yanayina na yi masa barka da zuwa ya amsa da kulawa yana fad'in.'' A kawo mini abinci Amina."
Ya kama hanya zai hau samansa da wata leda viva a hannunsa. Yaran gabad'aya suka fito daga kicin har da Mairo jin maganarsu ya sanya ya dakata ya tsaya aikuwa suka nufe shi da sauri ya rirri'kesu yana dariya suna ta jero masa sannu da zuwa.
Ina kallo ya dubi Khalil cikin nazari ya riko hannunsa yana fad'in." Kai matsalata da kai zurfin ciki da miskilanci ko akwai abinda yake damunka?"
Ya yi shiru yana sunkuyar da kansa. Karaf muka ji Minal na ce." Sultan ne ya mutu ko Hassana, shikkenan ya mutu, shikkenan ya mutu." Ta dinga fad'a tana tafa hannunta.
Na ji kamar an rad'e mini guiwata da tar'barya. Nusaiba ta fito daga kicin din ganinmu a tsaye ya sanya ta d'an daidaita yanayinta ta dan risina tana fad'in.''Baba sannu da zuwa?"
Ba a hayyacinsa ya amsa ba saboda maganar Minal ta dake mu gabad'aya sai Khalil ya fara hawaye. A lokacin ne ya kara kid'imewa yana fad'in." Sultan ne ya rasu Amina?".
Na ce." A a lafiyarsa lau me yasa za ka yarda da maganar yara." Ni kaina na fad'i maganar ne wadda nake da tabbacin cewa ba zai yadda da ita ba amma don ya gazagata na ce da Mairo ta kira Baba Tabawa.
Ta kuwa fito da yaron goye a bayanta na ce." Kwanto mini shi." Ta yi yadda na umarta tana gaishe shi ya amsa babu sukuni. Inda yake na nufa da yaron a hannuna yana ta bacci.  Na ce da yaran su je su yi sallar Isha'i su ci abinci da sauri suka bar wajan shi kuma ya kar'bi yaron muka haura saman a tare.

Leda viva dana kar'ba a hannunsa a lokacin da zai kar'bi yaron a hannuna na ajiye can gefa ya zauna da shi a hannunsa yana dudduba shi yake fad'in na dawo da farinciki sakamakon albishir din da Dr Sailuba ta yi mini Amina amma kuma me yasa za a yi mini a haka har yanzu a cikin gigita nake wallahi dalili ta yi mini bayani shima bai ji dad'i ba yana zazzabi hak'ori hakane ko?"
Na ce." E, yau tun safe ya tashi da zazzabin dalilin da ya sanya ni kiran Dr Sailuba kenan amma tsakani da Allah me yasa zaka yarda da maganar yara?"
Ya furta." Me yasa ba zan yarda ba lallai ne fa akwai abinda ya samu yaron nan ko ga yanayin yadda na ga tsoro da firgici a idon Khalil yarinyar nan Minal ba za ta yi karya ba."
Na ce." Ai ga yaron nan a hannunka ka duba shi sosai ka gani."
Ya kuwa fara duba shi har da cire masa kayan jikinsa ya bar shi da pampas yana jujjuyashi shi kuma sai dariya yake yi cikin ikon Allah zazza'bin ya sauka don dana ta'ba jikinsa babu zafi.
Na yi murmushi ina kallonsa na furta." Me ka gani a tattare da shi."
Ya saki ajiyar zuciya yana fad'in." Ban ga komai ba amma har yanzu ban yarda ba akwai abinda ake b'oye mini."
Na ce." Don Allah mu bar maganar nan mu yi wata ka ji."
Ya tsira mini ido na dan wani lokaci kafin na ji yana fad'in." Kin kyauta Amina ke ba za ki daina abinda ki ke yi ba ko?''
Nasan akan abinda yasa ya fadi haka na ce." Ka yi hakuri don Allah ina da ciki Dr Sailuba ta gaya maka ko?''
Ya gyad'a kansa yana cewa ta gaya mini amina amma mai yasa ki ke yi mini haka ba na fa jin dad'i tuntuni na gaya miki mai zai sanya abin alheri ya same ni a dinga b'oye mini wannan zalinci ne da d'aukar hakki wallahi."
Na ce." Ka yi hakuri ba zan sake ba."
Yaron na kar'ba ina mayar masa da kayansa. Shi kuma ya cire agogon hannunsa ya zare gilas din da hular kansa ya tashi tsaye tare da cire babbar rigar ya ajiye saman gado. Toilet ya nufa bai sake ce mini komai ba na sauka kasa da yaron na mayar dashi wajen mai rainonsa. Kicin din na nufa sun kammala komai na shirya masa abincin kamar yadda ya buk'ata da ya shigo
Na same shi yana sallar Isha'i na ajiye tiren a wurin da yake zama sai da ya jima saman daddumar yana addu'a kafin ya shafa ya taso yazo ya zauna na fara ko'karin zuba masa abincin yana ta kallona.
yana ci muna hira gidan Malam 'Daha da irin sallahun gaisuwa da godiyar da suka bashi zuwa gare ni. Nan yake yi mini bayanin abinda yake cikin leda viva da take ajiye gefe naje na daukota kayan dake ciki na fito dasu sassa'ken gargajiya ne da saiwowi gasunan kala daban daban. Ya fara yi mini bayanin yadda za a yi da ruwan rubutun dake d'aure a waya farar leda irin mai zurfin nan za a dafa maganin a tace a sha tsayin sati daya kullum karamin kofi d'aya. Babu maganar sauran asiri a tattare dashi kamar yadda malamin ya yi masa bayani matsalar dai aka samu har ta ta'ba masa lafiyarsa wannan mummunan d'aurin da aka yi masa tunda dama an yi shine akan manufofi da yawa. Idan har an dage da magani da kuma addu'a karfi da

mazantakarsa zai dawo fiye ma dana baya. Sai dai ya ce kada wata mu'amula irin ta aure ta wanzu har sai an gama shan maganin tukkuna.
Ai a daran ban bari gari ya waye ba na dafa maganin na tace shi sosai na zuba cikin wani dogon jug guda biyu na kai saman nasa na ajiye kullum da safe za a sha kofi d'aya idan ya yi karin kummalo.
Da safe kafin na fita falo Sahura ta kira ni a waya cikin annashuwa da farinciki take fad'in." Amina don girman Allah ki taya ni da godiya wurin Yallabai jiya na kar'bi takardar gidan da ya yi mini alkawari zai ba ni anan hotoro wajan ma'aikatarmu gida mai kyau Amina ginin zamani gashi ya sanya an zuba mini komai tarewa kawai zan yi."
Sai ta rushe da kuka.' har sai da na ji wani iri a raina na ce." Haba Sahura menene kuma na kuka don Allah ai kin wuce haka a wajenmu don girman Allah ki daina wannan kukan ba na so."
Na ji ta tana fad'in." Ya zama dole na yi kuka Amina na dad'i ne wallahi na rasa inda zan tsoma raina ba ki ga gidan ba mai yalwa da wadatattun d'akuna ga ababen more rayuwa kuma wai gidana ne mallakina."
Na ce." To menene a ciki ai komai rabo ne, ki godewa Allah kawai."
Ta ce." Shine abin godiya a koyaushe amma dai ya zama tilas na godewa wanda ya zama sanadi."
Sallama muka yi da ita ban kuma yi kasa a guiwa ba yanzu zan je na sake jadadda masa godiyata.

na kudi ne littafin don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Sai da na leka su Baba Tabawa tukkuna na duba Sultan ta yi masa wanka yana ta bacci cikin net dinsa muka gaisa sosai da su ina tambayar jikinsa ta ce ai ya warware sosai don jiya ma kwata kwata bai kwana da zazzabin ba har gari ya waye.
Na godewa Allah a cikin raina na fito saman zan nufa na samu Hauwa a kan kujera ita kadai a falo a zaune muka kalli juna na ganta a hargitse duk ta muzanta na janye idona da sauri daga kanta ai hausawa suna cewa.' Duk wanda ya hana uwarsa bacci to shi ma watarana bai zai rintsa ba kana ganinta kaga wadda take cikin tashin hankali da damuwa ashe tana son yaron ta cillar dashi ta tafi gashi yanzu 'kiri-'kiri tana kuka da nadama 'ya'yanta suna gudunta har dai mai suma saboda ta daukeshi Khalil da Minal kuwa ba na tsammanin ma suna yi mata magana domin duk gidan kamar mujiya haka ta zama.
Ina hawa saman ya ce na had'o masa shayi haka na sake sakkowa na shiga kicin na had'o kayan shayin na fito still dai tana zaune a kujera shiru ta d'an ba ni tausayi amma kadan ban kalleta ba na ji ta kira sunana na tsaya tare da dubanta.
Maganar dai jiya ta sake maimaita mini kada na gaya masa don ta d'auki sultan ya suma."
Na b'ata Raina ina fad'in." Wai me zai sanya na gaya masa ne Hauwa? me ki ka d'auke ni ne?" idan har ya san abinda ya faru to ki tabbatar babu yawuna

smma ai kin san a gaban yara aka yi kuma irin wannan lamarin da wahala ya 'buya."
Ta yi shiru tana gyad'a kanta ba ta ce komai ba. Na kad'a kaina kawai na haura saman da mamakin yadda ta yi sanyi ta zama wata Saliha bana tsammanin ma jiya ta rintsa saboda yadda na hangi tashin hankali a idonta.
Sai da na bari ya kammala shan shayin tukkuna na tsiyaya masa maganin a madaidaicin Kofi da kamar minti ashirin da biyar a tsakani ya sha maganin har yana yin gyatsa yana fad'in." Na gode uwar biyu.'
Na janye kayan tea din daga gabansa ina murmushi na ce." A madadina da Sahura muna kara godiya zuwa gare ka Ubangiji Allah Ya kara suttura da rufin asiri Allah Ya sa a mizani na gode sosai Allah Ya saka maka da alheri."
A tak'aice ya furta." Ni ma na gode sosai Allah Ya saka miki da alheri Ubangiji Allah Ya sa mu rayu tare har karshen numfashina."
Amin na furta. Ina kallonsa zuciyata na d'an dokawa kan zuciyata na sa'ko mini wani lamari na ji maganarsa yana fad'in." Yau Maryam ta cika kwanaki arbarin da rasuwa ko?"
Na ce." K'warai kuwa Nusaiba sun yi abin sadaka da sassafe su Masa'udu suka fita da shi zuwa bakin titi tana can tana baccin gajiya dakinsu baba Tabawa."
Ya gyada kansa a nutse Yana fad'in." Babu wani Abu da nake buk'ata a game da dukiyar matar nan Amina amma ya zama dole mahukunta suka shiga ciki tunda duka mun gama harhad'a abubuwan da ta mallaka ni da yaronta Salim sutturanta kuma na gayawa Nabila tunda har yanzu tana gidan a zaune tare da yaran Salim da Adam na ce su raba a tsakaninsu abinda ya danganci furniture na d'akunan gidan da na'urorin dake kicin dinta yaran sun ce a bar musu a gidan abinda na gada daga ciki na bar mu su. Wad'annan manyan kadarorin nata da kudin da muka gani cikin wannan dirowar tata sune alkali zai kasafta ba ni buk'atar komai na bar musu abinda dai nasan ba zan ta'ba yafe mata ba shine ko'karin mayar da ni rago mai rauni da ta yi. Idan har lafiyata da mazantakata irin ta d'a namiji ba ta dawo daidai ba Allah Ya isa ban yafe ba wallahi."
Na yi gaggawar danne dariyar da take so ta kufce mini sosai na daidaita yanayina don ganin yadda yake magana cike da alhini da saduda da damuwa.
Na daure na ce." Maryam ba kai kadai ta cutar ba my love har da ni fa."
Ya yi saurin kallona kafin ya gyara zamansa ya riko hannuna yana murzawa ya furta." Shiyasa ai kullum idan na yi sallah nake neman sakayya a wajan Ubangiji ta cuce ni Amina idan na gaza miki ta wannan fannin zan k'wareki kawaici da hak'urinki zai k'are nasan watarana za ki nemi hanyar rabuwa da ni saboda rashin samun wani babban lamari wanda ya tasirantu da gangar jikinki."
Na ce." Haba dai ka daina yin wannan tunanin in sha Allahu rabbi zaka samu lafiya ka ma fi da k'arfi da mazantaka kamar yadda malamin nan ya fad'a kai dai mu cigaba da yin maganin sau'ki zai zo in sha Allahu."
Rungume ni ya yi sosai a jikinsa yana fad'in." Na gode sosai matata tuntuni na gama sheda cewa soyayyar gaskiya ki ke yi mini amma ba na jin dad'i a

cikin raina a duk lokacin da na nemi ki na gaza kawar miki da bukatarki hankalina na tashi ina kuma tausaya miki a cikin zuciyata."
Cikin dauriya na ce." Babu komai fa kada ka tayar da hankalinka ina tare da kai duk rintsi in sha Allahu."
Ya sake matse ni tsam-tsam yana sauke ajiyar zuciya tare da sumbatar wuyana kamar dai koyaushe. Yana d'an yamutsa wasu wuraran na jikina.
Na janye a hankali Ina kallonsa yanayinsa ya canza sosai wanda yake nuna zallar buk'ata.
Ya dinga sauke nishi a hankali a hankali Ina kallonsa ya mike babu wani karsashi a tare da shi ya tafi ya je ya kwanta a gado. Yadda alamu suka nuna wannan shara'din da aka gindaya ya yi masa tsauri Allah kuma ya sanya ya iya jurewa zuwa sati dayan........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK.*
*07084653262*
*V-VIP AREWAPEN*
*138*
To a daddafe dai ya iya bari wa'adin da Malam 'Daha ya gindaya ya cika. Ranar da maganin ya k'are kamar ya zuba a ruwa a k'asa ya sha saboda murna abin ya dinga ba ni da dariya da mamakin yadda gabad'aya ya manta da cewar ba ni kadai ba ce matarsa akwai wata wadda son rai da rashin hakuri ya sanya yake take mata hakkinta. Yanzu tun ina jin haushin Hauwa wallahi ta fara ba ni tausayi domin kuwa tun daga ranar da yaron nan Sultan ya suma ta yi bala'in sanyi take neman shiri da ni kuma yanzu takan fito falo ta zauna idan ta ji motsinmu da yara da masu aikin ana wasa da dariya sai ta fito ta zauna tana bin mu da kallo tana d'an murmushi har idan an yi magana ta tsoma baki amma dai duk da hakan yaran nahiyar da take zaune basa kallo balle ma su je wurinta ta dinga jan Usai kenan da wasa ita kuma tana nok'ewa tare da zum'bura baki nata yaran Khalil da Minal bata yi musu magana balle kuma Sultan da baya son ganinta ko zama ta yi idan yana wasa sai ya rarrafa ya nufi wajen uwar rainonsa abin yana yi mata ciwo sosai. Amma babu yadda za ta yi haka gobe ma idan ta ji mu da yaran za ta sake fitowa.
A yau din ne da wa'adin ya cika kwanan turaka ya dawo hannunta duk da na lura duk ranar girkinta bata hawa saman yau kuma tun safe naga tana kai wa da kawo wa a falon ta hau saman har sau biyu. Sai na ji dadin hakan a cikin raina duk dai har yanzu ina jin tsoron kaidinta amma dai zan fi so su shirya su daina zaman gaba da k'ullatar juna tunda tuntuni sun riga sun zama abu daya.
Ban sani ba ko sun sasanta bai nuna mini alamar hakan ba tunda ai namiji ne yau zai ce baya son abu gobe kuma ya canza ya ce yana so kuma itama macace tana da nata dabarun na janyo hankali.
Na so dai a ce a yau din da yake ta gand'okin yin jima'i ya jarraba a kaina domin fita daga kokwanto da samun kwanciyar hankali dan gaskiya

damuwarsa ce kawai ta fito fili sai nake ganin na fi shi damuwa kawai ina dannewa ne.
Kwalliya ta yi sosai da yamma nuna tare da yaran a falo da yake Juma'a ce suna hutun makaranta ta fito ta dan zauna cikin mu na kamar minti talatin wajan biyar da arba'in ta haye saman tun daga lokacin ba ta sakko ba har da dare ya shigo na tashi na nufi d'akina domin gabatar da sallar magriba.
Na gama lazimina na dan jingina jikin gado zuciyata na d'an harbawa kad'an sai na tsinci kaina da shiga damuwa. Na sake rintse idona da k'arfi ina kiran sunan Allah ba ni so kishi ya jefa mini son rai a zuciyata idan har da adalci ya kamata a ce na bashi goyon baya wajan ganin ya yi hakuri  sun sasanta junansu. kuma daidai gwargwado ta yi hakuri ta jure kuma alamu ya nuna ta zubar da makaman ya'kinta neman shiri take yi ta sigogi da yawa. Amma dai duk da haka na so a ce yau din a yi gwajin a kaina ko don samun nutsuwar zuciya.
Sai da na yi sallar Isha'i tukkuna na ci abinci. Na samu waje na kwanta da wayata a hannu Ina d'an duba What'sapp dina amma dai still can kasan zuciyata sai dokawa yake yi ina mamakin ganin bai kira ni a waya ya nemi abinci ba kamar yadda yake yi idan ya dawo daga sallar isha'i wata zuciyar ta ce mini wata'kila bai shigo ba har yanzu shiyasa. Na girgiza kai ba na tsammanin hakan domin da ya yi sallar Isha'i yake shigowa sai da babban dalili yake sake fita idan ya ci abinci yakan dan duba Loptop din shi har zuwa goma na dare ko sha daya gaskiya ya shigo.
Ko dama murnar da yake yi kenan tunda sun jima ba su had'u ba dole ya yi marmarinta ya nuna gandoki. Idan kuma na tuna irin lugwigwitar da jikina ya sha a hannunsa a tsukin kwanakin da suka kasance na shara'din sai jikina ya yi sanyi na kasa gazgata kowane sashe na zuciya.

"Na gaya miki fa Hauwa na daina kwanciya dake saboda wannan dalilin na ji dad'i dake na dare daya ki dasa mini b'akinciki na shekara goma. Ban had'a shimfida dake ba balle ki d'auki ciki ki haife mu yi fad'a ki dire mini yaro ko yarinya ki tafi gidanku wannan shine hujjata." Ya yi maganar cikin kwanciyar hankali
A raunane ta ce." To yanzu ya kake so na yi na kai geji na rantse da zatin Allah ji nake yi kamar zan yi hauka a tsananin buk'ace nake rayuwata za ta shiga matsala."
A nutse ya furta." Ba ki yarda da hujjata ba kenan. Ba fa zan yi ba na gaya miki ki tashi ki fita kina 'bata mini lokaci zan yi aiki."
"Dan girman Allah ka yi hakuri kada ka jefa rayuwata a wani hali."
Ya dubeta sosai yana fad'in."  Kin ga na yi miki kama da wanda zaki karyawa rantsuwa Hauwa?"
Ta girgiza kanta cike da damuwa."
Ya ce." Ba zan yi kaffara akan ki ba, ki tashi ki ba ni waje idan kuma  za ki iya yi mini fyade Bismillah."
Tana kuka sosai ta furta." Allah mai ji ne da gani, kana zalintata kana tauye mini hakkina na rayuwar yau da gobe ba zan yi maka fyade ba amma sai Allah Ya saka mini tunda ni ba mazinaciya ba ce balle na je na nemi wani kai

kuma kana yi da matarka kuna gamsar da juna hakkina ba zai barku ba wallahi."
Dariya ya kama yi yana kallonta kafin ya ce." Ke ni fa ba wata lafiya na cika ba yanzu idan ma za ki daina shiga 'kunci akan ban kwanta dake ba itama Amina ha'kuri take yi Maryam ta kassara ni da asirinta.
Cikin rashin yarda da maganarsa ta furta." Wallahi ban yarda ba ai dama can haka ka ke yi mini ka jima kana zalintata sai Allah Ya saka mini."
A gajarce ya ce." Ni ma Allah Ya saka mini."
Ta tashi tare da kama hanyar fita ya bi ta da kallo ko daya bai tausaya mata ba domin ji yake yi har yanzu bai gama goge takaicin da ta cusa masa ba a baya.
Da asubahi ban kai ga tashi daga dadduma ba ya shigo da jallabiya da carbi tabbacin daga massalaci ya fito. Muka gaisa ya nemi gefan gadona ya zauna har da cire jallabiyar ya ajiye. Na ninke dadduma na ajiyeta a wajenta na zauna ina kallonsa a nutse na ce." Kwana biyu da suka wuce mun yi waya da anti Yagana tana gaya mini Dada bata da lafiya don har kwanciya ta yi a asibiti."
Da alhini ya ce." Me ya same ta?"
Na ce." Ciwon wuya ta yi amma dai da sauki an sallamota daga asibiti ina son zuwa dubata."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Ban 'ki zuwan ba amma legos nake so ki shirya mu tafi cikin satin nan da zamu shiga."
Na ce." Da dai ka d'auke mini zuwa legos din nan tun da kaga a halin da nake ciki ya kamata na zauna waje d'aya na samu nutsuwa ku je da Hauwa kawai."

Ya d'an Harare ni kafin ya ce." Dake zan je Hajiya ba wani dadewa za mu yi ba in sha Allahu mu dawo cikin yaranmu mu je mu huta ni dake na wata d'aya sannan akwai ayyukan da nake so na gabatar a can din."
Shiru na yi ina kallonsa tare da raya abubuwa da yawa na yi masa maganar Hauwa yana hararata kuma bayan tare suka kwana nuna mini yake yi har yanzu ba su daidaita ba.
Ya ri'ke hannuna yana d'an janyo ni jikinsa yana cewa." Jiya me yasa ba ki zo ba?"
Na ce."Me yasa zan zo? Don girman Allah ka daina wasa da tunaninmu yanzu don ka sasanta da Hauwa shine abin yi mini boye-boye na fi kowa farincikin hakan wallahi."
Ya fara ko'karin cire mini hijabin jikina yana fad'in." Ni na gaya miki haka Amina kada ki yi mini rigima a irin wannan lokacin da nake tsananin kewa da bukatarki kada ki yi abinda zai dakusar da farinciki da karsashina my love.."
Ya fara sumbatar sasssan jikina a mutukar dimauce yana yin wani irin numfashi bakina ya mutu murus domin abinda jikina yake marari ne ya samu da na yi yun'kurin yin magana da turjiya sai na ji bakina ya yi nauyi bayan sa'kkonin soyayyar da yake aika mini ta kowace ga'ba. Bakinsa ma amayarwa yake yi tare da wata irin sheshsheka haka muka kasance cikin ru'kun'kumar juna zuciyata na ta tsalle ido a lumshe can kasan zuciyata ina

ta kiran sunan Allah da ro'kon Allah wanzar da alheri akan abinda za mu yi Ubangiji maji ro'kon bayinsa wata iriyar rayuwa muka yi wadda ta ki'dimar da mu. Kuzuri da nagarta da mazantaka abin sai godiyar Allah da sake jaddada addu'a ga Malam D'aha da zuri'arsa kamar yadda ya fad'a mun ga zahiri domin kuwa ni zan tabbatar da cewa karfinsa na d'a namiji ya ninka na baya kafin a yi masa d'aurin goro.
Muna gamawa ya dinga godiya ga Allah har sai da ya ba ni tausayi a d'akina ya tsarkake jikinsa yana fad'in." Amina zan iya mallakawa Malam D'aha rabin dukiyata domin wallahi ya taka muhimmiyar rawa ga rayuwata na riga na sare fa ban ta'ba tsammanin mazantaka zata dawo ba sai gani rass da ni ki gaya mini ya ki ka ji don Allah."
Ya fad'a yana kanne idonsa daya.
Ni ma cikin tsokana na ce." A  wallahi ras da kai Baba gaskiya ka yi bajinta Allah Ya sakawa da Malam 'Daha da alheri ya cancanci komai daga wajenka
Ya riko ni yana fad'in." A hankali duk zan biya ki bashin da na ci miki ko?"
Cikin nuna ya yi kokari na ce." Haba ai tun jiya ka biya ni Allah Ya taimake ka, a ai sai da na ce alhamdulillahi."
Ya kuwa fashe da dariya yana sake rungume ni a jikinsa.

Na kudi ne littafin nan kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

To a haka na yi kwana biyu na muna morar juna  da nishadi ranar da Hauwa ta kar'bi girki kuwa ya rasa gane inda ba dosa tunda na hau na gaishe da safe ban yadda mun sake had'uwa ba marigaba na yi na shige d'akina na kuma kulle kofata duk da nasan aikin banza na yi yana da mukkulin d'akin amma dai hakan zai fi mini kwanciyar hankali ya kwana shi kadai idan ma ba zai kwanta da ita ba.
Babu kalar rarrashin da bai yi mini ba ta waya na ce ba da ni ba wallahi duk yadda nake jin zafinta a raina ba zan yadda ya had'a kai da ni a zalinceta ba to ballantana ma yanzu da da ta sauko take neman shiri ba na jin haushinta amma fa na ki sakin jikina da ita.
A haka muka cigaba da rayuwar a gidan har ya ha'kura ma duk ranar girkinta baya nema na ban san dai ya suke 'karkewa ba tunda nakan dan ganta jefi jefi ta hau saman  a ranakun da take da girkin ta kara ramewa kwarai da gaske ta zama silent ma kamar ba Hauwan da na sani ba mai neman fitina da son kin zaman lafiya. Kuma har yanzu jiya I yau tsakaninta da 'ya'yanta sai dai ido idan ma ta kira su wajenta Minal dai ba ta zuwa Khalil ne koda zai je a cikin fargaba da shakku yake zuwa  saboda ta saba dukansa."

"Hauwa Legos za mu tafi ni da matata ban hana ki zama ba tunda kina ganin za ki iya amma wallahi tallahi kada na ji kada na gani akan yarana da wanda ki ka haifa da wanda ma ba ki haifa  ba lafiya lau za mu tafi mu bar basu da masu yi musu hidima duk abinda ya faru a gidan nan zan yi kuka dake kuma zan yi miki hukunci mai tsananin gaske."

Ta ce." Hukunci ya wuce wanda kake yi mini a yanzu. Ni ina ruwana da yara kuma abinda ya dame ni daban me zan yi musu ai ni ba azzalima ba ce."
"Na dai gaya miki domin na san halinka ba ki da mutunci babu ruwanki da kowa."
Ta fashe da kuka tana fad'in." To na ji, yanzu sai ka gaya mini menene makomata ai ba maigadi ba ce ni. Wane irin zalinci ne wannan kake yi mini 'kiri-'kiri an raba da ni da yarana suna k'yamatata ai duk tsiya ba za su canza ni ba."
Shiru ya yi mata. Ta cigaba da cewa." Ka gaya mini menene matsayina gaskiya na gaji wallahi, Allah kuma yana ji yana gani."
Ya dube ta sosai tare da cewa." Na yi na yi na ga na ha'kura na yafe miki na kuma sanyawa zuciyata sonki da kaunarki amma kin san Allah babu waje a cikin zuciyata da farfajiyarta Amina ta shimfida mashinfidinta ta zauna daram da can Samira tana da waje amma yanzu Amina ta mayaye ko'ina ita kadai ce a ciki ba kuma na tsammanin har abada wata maccan za ta samu irin wannan sararin."
Ta dinga wani irin kuka mai tsuma zuciya da sosai rai wanda duk wanda ya ji sautinsa sai ya tausaya mata amma a wajensa ma damunsa take yi so yake ta tashi ta fita ta bar masa d'akinsa.
"Ni ba zan ta'ba yi maka irin wannan 'kiyayyar ba domin ko banza mun had'a jini kuma na haihu da kai yara uku duk irin cin fuskar da za ka yi mini da tozarcin da za ka yi mini ba zai dame ni ba, hakkina dai da yake rataye a wuyanka wallahi ba zan yafe maka ba, ka zalince ni kana k'untata mini kuma ba zaka sawwa'ke mini ba idan an yi duniya don manzon rahama ba zan sake nemanka ba."
Ya ce." Hakan ya fi miki Hajiya ai ban hana ki ba idan kina da kwanjin da za ki kwaci hakkin na ki bismillah ai ga ni a zaune."
Ta tashi jiki a sab'ule ta kama hanyar fita kamar zata mutu saboda b'akinciki.
Har ga Allah ba na jin dad'in fuskar gizagon da yake yi wa Hauwa gabad'aya duka kowa ya gane Hauwa bora ce a gidan zaman ha'kuri take yi masu aiki duk sun gane irin zaman da suke yi da ita da maigidan. Abin ya dinga damuna a ganina ai shi ne namiji kuma jagora ce ya ci ace ya tsahirta da wannan tsatstsauran hukuncin da yake yi mata ta dahu lugub ta yi mugun laushi ta kuma tsunduma a cikin nadamar abinda da ta aikata. Shine bai sani ba ko kuma na ce ya sani yana takewa amma mugun zunubi yake nannagawa kansa domin wannan fad'in Annabi Muhammadu S.a.w ne.
Wannan dalilin ya sanya ni ranar da za mu tafi Legos din da daddare na shiga d'akinta na sameta a zaune ita kadai kan gado ta kunna tivi amma gabad'aya hankalinta ma baya kanta kuka take yi tana waya ganin shigowata ta katse wayar tana share hawaye na yi kamar ban lura ba.
Na zauna gefenta muka gaisa na ce." Ya gaya miki Legos za mu tafi gobe ko?''
Ta ce." E, ai jiya mun d'an jima muna magana da shi akan tafiyar taku.".
Na d'an yi shiru Ina nazarin maganarta wadda na tabbatar da cewa 'karya ce kawai wai ita dole sai ta nuna mini suna shiri bayan komai a bayyane yake.

Na ce." Ai da so na yi ku tafi tare idan kun dawo zai sake komawa sai mu je kamar hakan zai fi."
Ta yi ya'ke tana cewa." Duk daya ne Amina ku je tare ni zan kula da yara kamar yadda jiya ya gaya mini cewa ya ba ni amanarsu za ku dawo ku same su lafiya in sha Allahu."
Kamar zararriya haka take magana a tsorace tunda tasan duk abinda zata fad'a ba gaskiya ba ne shiyasa ta kasa had'a ido da ni.''
Na ce." Hakan ya yi Hauwa dama na ce bari na shigo mu yi sallama tunda da wuri za mu tafi wata'kila kina bacci a lokacin."
Kanta a 'kasa ta ce." Hakan ya yi na gode sosai Amina sai kun dawo din.''
Na mike tsaye ina fad'in." To saduwar alheri Hauwa sai mun yi waya." Daga haka ban sake cewa komai ba na kama hanyar fita zuciyata da damuwar halin da take ciki kada fa mutumin nan ya zautata da bak'incikinsa domin duk ta shiririce wallahi........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK.*
*V-VIP AREWA PEN*
*07084653262*
*139*
Ba na tsammanin ya yi sallama da Hauwa da za mu tafi haka na bi shi  ba don zuciyata ta so abinda yake aikatawa ba sai don sanin rashin yadda zan yi da shi. Tunda tsakani da Allah daidai gwargwado yana da ilimin addini ya kuma san abinda yake yi din ba daidai ba ne. Na zura masa Ido kawai domin nasan muddin bai gyara ba Hauwa za ta sake tafiya gidansu mahaifiyarsa kuma ta samu labari anan sai ta gane cewa shima ya fi kyarfinta ba Hauwa ba ce kad'ai mara ji shima lamba d'aya ne.
Zuwanmu legos ya sake haifar mana da nutsuwa da kula da juna da kuma bud'e babin soyayya kamar sabbin aure duk da 'karamin cikin da nake d'auke da shi bai hana mun mori juna ba
a duk lokacin da ya zo wajena da buk'ata irin ta d'abia. Daga lokacin na gama gazgata k'aunar da yake mini cewa babu algus ko almundahana domin duk wani nau'in kulawa ina samu da tarairaya har da kyautar kud'i miliyan biyar ya yi mini yana gaya mini na kara akan kasuwancin da nake yi domin yana hankalce da irin nauyi da d'awainiyar da nake yi a b'angarena.
Na yi godiya sosai da addu'ar k'ara samun budi da fatahi ya ce babu godiya a tsakaninmu a duk lokacin da nake da buk'atar kudi domin yin wani abu da zai kawo mini cigaba zai tallafa mini saboda yana girmama duk wani wanda yake tsaye don dogaro da kansa karin abin kuma ina ko'karin ganin na yi alheri da taimakawa wad'anda na fi su wadata.
Na ji dad'i sosai da sosai dama kuma mun yi magana da anti Yagana akan jari da zan bata ta yi sana'a ta ce mini tana so ta bude shagon jikin gidanta ta fara harkar provision da awo na ce mata harka ce mai kyau sosai kuma za ta samu alheri domin yanzu masu sayar da abinci kayan masarufi sune suke da kudi a hannu. Abinda na yanke a raina cewa ita zan turawa kudin gabad'aya

ta fara idan Allah ya sanyawa kasuwancin albarka sai ta zama babbar dila ta bud'e manyan shaguna. Sai dai abinda yake dan damuna shine shin kudin da ya ba ni zai bawa Hauwa ko kuwa. Ina sonsa ba kuma zan yi farinciki da cewa ranar lahira ya tashi a cikin sahun mazan da za a yi musu azaba dalilin fifita bangare daya na daga cikin matansu.
Kuma daidai gwargwado Hauwa ta kar'bi kuskuranta yau satin mu uku a Legos idan ba ta kira ni a waya yau ba to gobe za ta kira ni mu gaisa a sati sai mu yi waya biyar ko hud'u mun yi vidiyo call sau d'aya da ita kuma ban hangi nutsuwa da kwanciyar hankali a tare da ita ba. Abinda na fahimta shine kamar tana kamun kafa da ni akan mijin nata wanda ni kuma nasan ban isa na sanya shi ko na hana shi ba tunda ga abinda ya yi wa mahaifiyarsa na yaudara ya nuna mata kamar ya ha'kura ashe akwai abinda ya ajiye a ransa na ramuwar gayya.
Na dinga nanata masa kan cewa yadda ya ba ni kudin nan Hauwa ya bata hakkinta ne. Na farko da na gaya masa shiru ya yi mini bai ce komai ba ya cigaba da sabogoginsa tunda ya ce mini yana shirye-shiryen bud'e sabon kamfanin na suminti ne wanda suka yi tarayya da yaran Alhaji Amadu abokinsa Salim da Adam da Nusaiba. Yana so ya fara sanya Salim din cikin harkokin da yake gudanarwa domin ya tsaya da kafarsa a matsayinsa na namiji babba da ake sanya rai a nan gaba zai zama wani abu. Mahaifinsa Alhaji Amadu harkarsa kenan sayar da siminti da sauran abinda ya danganci gini gidaje to shine yake so ya d'ora yaronsa a kai.
A k'alla dai sai da na yi masa maganar Hauwa ya kai sau shida tukkuna ya tanka mini da tashin hankali ya rintse idonsa yana gaya mini babu ruwa da duk abinda yake yi na dawo masa da kudinsa idan ba na so tunda bai isa ya yi mini kyauta na ce na gode ba sai na yi masa gyara saboda na mayar dashi jahili Wanda ba shi da addini.
Na kuwa bud'e wuta ni ma na ce ai gaskiya ce kuma d'aci ne da ita ban iya munafurci ba kuma zan yi masa shiru ya danne mini baki da kudi mu zalinci wata ba domin ba ni so na mutu da hakkin kowa.
Ya ce idan akan Hauwa nake yi masa rashin kunya sai ya saketa kowa ya huta.
Na ce masa dama hakan ya yi shi zai kara tabbatar mini da cewa babu wanda ya isa.
Magana ce mai harshen damo ya tsargu sosai daga ranar da muka yi haka ya daina kula ni tsayin kwana uku muka yi ba ma magana gashi Muna kwana a d'aki daya a gado daya sai da ya juya baya ni ma na juya nawa.
A ranar na hud'u ne muna bidiyo call da Hauwa na ce mata ta had'a ni da yaran mu gaisa na yi hakane domin na daidaita alakar da take tsakaninsu..
Aikuwa da azama ta tashi ta fita falo alhamis ce babu islamiyya ta yamma ina zaune ina kallonta ta shiga dakinsu tana Kiran sunan Khalil.
Ya zo ya zauna a gefena ban ce masa komai ba shi ma bai ce mini komai ba amma dai tun shekaran jiya na fahimci jikinsa ya d'an yi sanyi ya rasa yadda zai yi ya rarrashe ni ya kuma nuna zai gyara kuskuransa.

Daya bayan d'aya muka dinga gaisawa suna ta tsalle da dariya mussaman Minal sai washe baki take yi. Ya yi gyaran murya yana fad'in." Ni ba bu wanda yake nema ko?"
Jin muryarsa ya sanya suka dinga kiran sunansa." Baba" Baba.'' Ya kar'bi wayar ya haska musu fuskarsa sai dariya suna kiran sunansa yana amsawa cikin nishadi yana cewa ni babu wanda yake nema na ko?"
Usai ta ce." Baba yaushe za ku dawo?"
Ya ce." Mun kusa in sha Allahu ana zuwa makaranta ko?"
Suka ce "Eh.'' Ya gyad'a kansa yana fad'in." Muna nan dawowa in Allah Ya yarda."
Hauwa ta kar'bi wayar daga hannun Khalil tana hasko fuskarta ta ce masa "Ina yini?'' Ya amsa da sakin fuska har yana tambayarta yara."
Cike da jin dadi ta ce." Gasu nan ai suna ta kewa" a Takaice ya ce." Mun kusa dawowa amma ke ba ki yi kewar ba."
'Yar dariya ta yi kamar an yi mata dole ta ce.'' Sosai na yi kewar ku gabad'aya."
Ya yi murmushi a hankali ya ce." Duk ranar da na yanke mana dawowar zan sanar dake."
Da jin dadi ta furta." To shikkenan." Ya mik'o mini wayata na kar'ba muka d'an yi magana da ita akan yaran sannan muka yi sallama tare da bata sakon gaisuwa wajan masu aikin gidan.
Na kashe wayata na ajiye ban dube shi ba na sake hade raina sosai domin har yanzu ina jin haushin bala'in da ya yi mini sai kace 'yar cikinsa daga kawai an ce gaya kayanka.''
Ya riko hannayena duka biyun na dube shi amma ban saki fuskata ba. Sai ya sanya hannunsa d'aya a kumatuna yana ta'be mini fuska da hanci yana d'an murza mini fatar le'be. Tankwa'be hannunsa na yi ya sake mayarwa ya cigaba da ta'bule mini kumatuna da hanci na sake cire hannunsa a karo na biyu.
Ya sauke ajiyar zuciya a 'dan sanyaye ya ce." To ki yi dariya mana tunda na yi magana da ita?''
Juyar da kaina na yi gefe ban ce masa komai ba. Ya matso sosai yana fad'in. Ki yi dariya my love menene haka umm!
Na ce." Wallahi ka ba ni haushi sosai wai me kake ji idan kana gaba da mutum ne babu kyau fa kuma ba abin burgewa ba ne saboda kawai na baka shawara ka gyara sai ki dinga fad'a mini magana zagi na ne fa kawai ba ka yi ba."
Ya d'an yi shiru na wani lokaci kafin ya furta." Na gyara daga yau idan hakan zai kasance farincikinki shikkenan ko?"
Shiru na yi tare da ta'be bakina ya juyo da fuskata yana fad'in." Mu yi soyayya ko?''
Ban ce masa uffan ba ya d'ora kansa a saman kirjina tare da zagaye k'unguna da hannayensa yana sakin ajiyar zuciya.

Tun daga ranar Hauwa take yi mini vidiyo call a ranakun da yaran suke gida ta had'a ni da su mu jima muna hira. Wannan dabarar ta kara mata kusanci

da su kwarai da gaske na ji dad'i sosai kuma ina sa ran nan gaba duka za su manta da abinda ya faru su d'auketa a matsayin uwarsu kamar ni.
Ranar litinin da daddare muka yi waya da ita take gaya mini ai maigidan ya sanar da ita cewa za mu dawo alhamis nan da kwana uku kenan. Na ce mata eh haka ya gaya mini ni ma. Mun jima muna magana akan yara tana labari yanzu Sultan na yarda ta d'auke shi yaran kuwa gabad'aya sun daina gudunta. Cike da jin dad'in hakan na ce dama ai sakarci ne irin na yara cikin ko'karin nuna mata kuskuranta na baya na ce ai shi yaro baya son hantara da kyara duk inda ake dukansa ko aka nuna masa tsana zai guji wajen kuma kwakwalwarsa bata saurin mance abu.

To a daran ranar da za mu tafi sai ga wayar Idiris mijin Sahura muka gaisa da shi sosai ya fara gaya mini dalilin da ya sanya ya kira ni cewa Sahura ta tare a sabon gidanta kuma ya sanya kwa'do ya kulle tsohon wanda na mallaka mata ya yi-ya yi da ita ta bashi aron gidan ya sanya amaryarsa ta ce 'yan haya zata zuba. Da farko ya kama hayar d'aki daya da rumfa mutum biyu ne a gidan da ya kama hayar to dakunan k'ananu ne gashi iyayen amaryatasa sun yi mata kayan d'aki a matse suke a gidan. Shine yake neman alfarma a wajena na yi mata magana ta d'an ba shi aron gidan su zauna shi da amaryar tasa na d'an wani lokaci.
Na yi dariya sosai har sai da jikinsa ya yi sanyi ya dinga fad'in.'' Amina dariya ki ke yi mini tsakani da Allah daidai ne abinda Sahura ta yi mini ai mun zama daya ni da ita kuma ban auri yarinyar nan domin na wulakantata ba Allah Ya kaddara ne kawai."
Na ce." To Idiris gida dai na mallakawa Sahura shi tuntuni ka ga ba ni da hurumin da zan ce mata ga yadda za ta yi da shi tunda yanzu mallakinta ne ai daidai ne idan ta zuba 'yan haya ba wata matsala ba ce."
Ya furta." Ai na buk'aci cewar ta ba ni hayar gidan ta ce wai ita na waje za ta bawa domin tana zargi kada shekara ta zagayo na 'ki biyan ta wanda ni babu hakan a cikin raina wallahi zan biya ta kud'inta dalilin da ya sanya kenan na kira ki idan ba za ta sanya ni domin Allah ba to ki rarrasheta ta ba ni haya ta fad'i abinda ta yanke da shedu da komai a tsakani duk shekara na biya ta kud'inta.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*140*
Na yi 'kokarin danne dariyar da yake ba ni na ce." Idiris a yanzu dai ba ni da wata hujja mai karfi da zan ce da Sahura ta baka gidanta ka sanya amaryarka a ciki. Akwai gidajen haya da yawa a unguwanni mai zai hana ka

sanya dillalai su cigita maka sai ka biya hankali kwance ka sanya matarka a ciki ina ganin kamar hakan zai fi kwanciyar hankali."
Ya yi d'an jim kafin ciki kame-kame ya fara cewa" To shikkenan zan sanya a nemo mini din amma tunda ita ta ce haya zata bayar da gidan mai zai hana ni ta ba ni akan dai ta bawa wani na waje kuma tsakanina da Sahura ai mun zama dayai shekaranmu kusan ashirin da aure yana da kyau a ce ta gane yadda take da matsayi a cikin raina. Karin auran nan na gaya mata nufin Allah ne amma ta ki kwantar da hankali koyaushe idan na je gidanta da rigima muke rabuwa abubuwan nan da take yi mini bana jin dadi wallahi."
Na furta." Sai a hankali za ka ga komai ya wuce amma ni dai a shawarce kawai ka bar mata gidanta ka nemi wani."
Ya amsa da "To a sanyaye muka yi sallama na kashe wayata na ci dariya na koshi lallai Idiris ba shi da kunya wato shi gani yake yi abinda ya yi wa Sahura 'karamin abu ne da bai kamaci ace ta daga hankalinta ba ana sa tunanin kenan kuma yanzu Allah Ya dube ta ya kawo mata d'auki ya lallabo su ci tare har yana so su samu sakewa da walwala da matar da ya auro a kuma cikin gidanta. Shi dai kawai ta bashi ya sanya matarsa a ciki amma babu maganar biyan kudin haya fad'e kawai yake yi mahaukaci ne shi ya d'auki kudi ya bata bayan yana ganin gidajen duka samunsu ta yi a sama ba kudinta ne ya saya mata ba. Ni kaina ba ni goyon bayan hakan domin yadda yake munafikin nan ta sanya shi a gidan watarana sai dai mu ji labari ya sayar mussaman idan ya sake tara yara wahala ta sake yi masa yawa. Kuma dole ta ha'kura ta kyaleshi dalilin yaran da suka ratsa a tsakaninsu .
Daga na yi juyi sai abin ya fado mini nasa dariya har sai da shigo gidan ya fahimci Ina dariya jefi jefi ya fara tambayata menene na bashi labari yadda muka yi da Idiris din.
Tsaki ya ja yana fad'in shima baya goyon bayan hakan tun daga farkon fara neman auran da rikicin da suka dinga yi ya gama fahimtar shine bashi da gaskiya kuma ai duk matar da za a yi wa kishi miji yakan ru'banya kulawa da ita domin dakushe mata damuwa da takaicin abokiyar zamar da za a kawo mata amma shi bai yi ko daya ba ya kuma nuna abinsa nasa ne shi kadai abinta kuma nasu ne gabad'aya muguntà ce tsantsa irin ta wasu mazan.
To alhamdulillahi cikin hukuncin Allah muka isa abuja muka samu gida da jama'ar dake cikinsa cikin farinciki da murnar dawowarmu tun daga kan Hauwa zuwa yaran da masu aiki kowa bakinsa har kunne . Sosai na ga can ji mai kyau tsakaninta da su Taburni da akwai girmamawa da kuma mutunta juna. Na ji dadin hakan na yi addu'a a cikin zuciyata Allah ya sanya hakan ya d'ore.
Kwana biyu ita take dawainiya dashi ya d'an sake da ita babu kallon kyama ballantana hantara kuma bai nemi da na zo na yi masa wani abin ba har sai da ta yi kwana biyunta tukkuna sannan na kar'bi hidimar tasa.

Ranar da muka cika sati daya da dawowa Sahura ta kira ni a waya muka gaisa jin muryarta a cunshe ya sanya ni saurin tambayarta nan take gaya mini Idiris ya sanya an 'balle k'wadon da ta kulle gidanta sun tare da matarsa

a ciki itama d'aya daga cikin yaran shagona ne yake gaya mata shine take gaya mini zata d'auko masa 'yan hizba.'
K'warai na yi mamakin da jin haka wane irin karfin hali ne da Idiris ne shin ina kudin da ya samu to ai ba zai ce duka miliyan takwas din ce ta kare gabad'aya wajen neman auran matarsa ba. Lallai bai so zaman lafiya ba domin duk da take matarsa tana da 'yancin da za ta nemi hakkinta wace irin gadara ce wannan da son rai."
Ta fashe da kuka tana fad'in." Amina wallahi saboda yara nake zaune da Idiris ba na so na kunyata Yallabai dan ganin irin tagomashin da ya yi mini amma wallahi na gaji da guma mini takaicin da yake yi hizba zan kai shi kwanaki fa haka ya kira baban yayanmu Alhaji Rufa'i yana gaya masa wai gaba nake yi dashi saboda ya k'ara aure na daina bashi hakkinsa na auratayya sannan ina fita ba tare da izininsa ba idan na yi abinci bana zuba masa idan ya zo gidan wallahi kuma sharri ya yi mini. Abiñci wataran ba shi yake yin cefane ba ni nake yin abina aiki kuma dole na fita tunda dama tuntuni shine yake ri'ke da ni da yara a gidan da bana fita aiki da ba mu kai labari ba. Maganar kwanciyar aure kuwa tuntuni na ajiye a gefe bana kaunarsa wallahi shiyasa ko sha'awar ya zo kusa da ni bana yi."

Na ce." Lallai Idiris ashe bai d'auki shawarar da na bashi ba kenan. Kwanaki fa ya kira ni yake gaya mini kin hana shi gida kin sa kwa'do kin rufe wai na yi miki magana ki bashi hayarsa domin kayan d'akin da aka yi wa amaryarsa suna da yawa can inda ya kama mata haya ya yi matsatsi ya ce ki yanke kudin da zai biya wai na zama sheda duk shekara zai dinga biyanki."
Ta ce." 'Karya yake yi wallahi ta 'karfi da ya ji yake so na bashi gidan akan ban bashi ba ya ce sai dai na ajiye aiki ni kuma na ki ajiyewa shine fa ya gaya yayanmu wai ina fita yawon ma'kota da zuwa kasuwa cefane bada yawunsa ba. Sannan ya bi dare da rana ya buge kwadon da na sanya ya shiga gidan da matarsa suna zaune yau kwana hud'u kenan."
Dariya kamar cikina zai ciwo bakina ya mace na kasa ce mata komai saboda dariyar da nake yi ta hana ni maganar har sai da na ji maganarta a fusace tana auno mini zagi!
Na danne dariyar sosai ina fad'in." Sahura Idiris takadirin mutum ne wallahi malam bahaushe tsantsa to ki kai shi hizba ki kai wa Sahura an zama daya fa ba zan baki shawarar kai shi hukuma ba don Allah ki rabu dashi wallahi muddin yana zalintarki Allah zai saka miki."
Ta ja hanci tana fad'in." Sai fa hukuma ta shiga cikin lamarin nan Amina na rantse da Allah ba zan lamumci wannan rashin mutuncin ba."
Na ce." Idan kin kai shi hizba suka tura ku kotu ai kin ga duniya ta ji kuma akwai manema labarai ko babu komai mu kyale shi ya ci darajar su Yusra mana Sahura. Kuma a jikina nake jin idan kin kai shi hukuma zai kara fusata ya ce dole ki ajiye aiki kin ga an biyu babu ko?"
Ta yi shiru tana sauke ajiyar zuciya irin ta b'akinciki da takaici can kuma na ji kittt ta kashe wayar na shiga duba wayata da mamakin abinda ta yi wato bata ji shawarar da na bata ba kenan. To Allah Ya rufa asiri.

***

Wata uku a tsakanin dawowarmu daga Legos cikin da yake jikina ya d'an tasa zuwa yanzu wad'anda muke tare da su a cikin gidan sun fahimci ina d'auke da juna biyu tunda har ya huda zani ya yi kurcici wata biyar kenan ba wasu kwanaki.

K'warai da gaske na yi mutukar mamaki ganin sauyin fuska da mu'amula daga Hauwa sabanin lokacin da muka dawo tana masifar haba-haba da ni da son shiga lamarina da kuma yawan yi mini hira idan muna falon gabad'aya amma tun sa'ilin da ta lura da cikin da nake d'auke shi ta sauya fuska ta kuma rage shiga jikina. Ba mu yin gaba dai tunda tana gaisheni kullum da safe ko da ban fito falo ba ta kan biyo ni dakina mu gaisa amma ba ta zama daga tsaye idan mun gaisa sai ta fita. Ta rage zaman falon sosai ta tsiri na d'aki tunda dama da'biarta ce idan tana nukufurci da jin haushi sai ta rufe kanta a d'aki sai ta ga dama take fitowa.

Jikina ya yi sanyi sosai ganin halin k'uncin da ta shiga duk saboda ina da ciki menene abin damuwa ga matar da take da cikin haihuwa kuma take da mijinta a hannu. Don na d'auki ciki itama rabo yana rantsewa za ta d'auki nata abinda dama maigidan yake buk'ata kenan ni da ita har yanzu ba mu wuce haihuwar ba to ban ga abinda zai sanya ta daga hankali ba a ganina ni zan yi wannan damuwar tunda ta d'ara ni da 'daya har da namiji a ciki ni kuwa nawa duka mata ne kuma ban yi mata ganin kyashi da kishi ba.

Ana haka maigidan ya tafi bunkure dalili an fara gudanar da aikin rushe gidan Malam D'aha kamar yadda ya yi alkawari zai sabunta masa gidan da gini na zamani kuma zai gyara masa tsangayunsa. Ya ce mana zai yi kwana uku ko hud'u domin bayan ya gama da gidan Malam D'aha zai gudanar da wasu al'amuran da duba ma'aikutunsa da suke jahar.

Washe garin ranar da ya tafi ta yi bakuwa. Kallo d'aya na yi mata na sheda ta 'yar uwar nan ta ta ce da muka yi wani zuwa garin nasu domin gaisuwar mutuwa wadda ta dinga shige da fice tana kallona a lokacin har sai da ta magantu.

A falo ta zauna tunda lokacin da ta shigo duk muna zaune a falon gabad'aya muka gaisa sosai da ita ban nuna mata komai a fuska ba take fad'in wai Seminar suka zo garin shine ta ce bari ta zo mu gaisa..

Cikin raina na ce ki gaisa dai da 'yar uwarki. Anan falon ta ci abincin da na sanya Baba Tabawa ta kawo mata sai da la'asar ta yi tukkuna suka tashi suka shiga d'akinta tare.

Ni ma a lokacin na tashi na shiga d'akina domin yin alwala.

Ina idar da sallah da kamar minti biyar kira ya shigo wayata na daga a nutse na gaishe shi ya amsa yana fad'in." An ce mini kun yi ba'kuwa ko?'"

Na ce." E, bak'uwar Hauwa ce daga bauchi ta zo wata Seminar ne nan."

Ya furta ya sunanta?" jim na yi kamar Sadiya na ji tana kiran sunanta. Ya ce." Ba ni son shige da fice ya yawaita idan ba na gari ku kula sosai."

Na ce." In sha Allahu rabbi ranka ya dad'e." Ya d'an saki ajiyar zuciya yana fad'in." Idan na gama abinda nake yi anan zan wuce maiduguri domin duba Dada ba ki da sa'ko?"

Na ce." Kash! amma ba ka kyauta mini ba wallahi tare fa muka yi da kai za mu je shine zaka zame ka yi tafiyarka kai kadai."
Ya furta." Ki bari ki haihu ki samu lafiya sosai sai ki je in sha Allahu."
Na ce." Shikkenan yaushe za mu yi tsammanin ganinka ?"
Ya d'an yi jim kafin ya furta nan da kwana uku in sha Allahu."
Na ce." To shikkenan Allah ya dawo mana da kai lafiya."
Ya amsa da Amin ki shafa mini kan yarana gabad'aya a ce ina gaishe su."
Ina dariya na furta." Zan gaya musu in sha Allahu rabbi."
Sallama muka yi na ajiye wayar ina murmushi wanda na kasa tantance ko na menene.
Yau su Baba Tabawa Jallof suka yi na shinkafa da tafiya sai suka yi amfani da bushashan kifi ta ji alayyahu da albasa ta yi kyau ainun a ido kuma na tabbatar da cewa za ta yi dadi amma bata ni sha'awa babdon ko da ta kawo ta ajiye mini ita a gabana sai na ji tana tashin karnin kifi wanda na tabbatar da cewa hancina ne kawai da kuma tsagunaguni na mai juna biyu.
Ko loma daya ban iya ba na ce ta d'auke plate din ta yi yadda nace din ta zo tana tambayata ko akwai abinda nake buk'ata tunda da sauran dare sai ta yi mini."
Na dube ta tausayi suke ba ni dattijan kwarai da gaske har gwara Taburni ta haihu har da jikoki ita kuwa Baba Tabawa bata ta'ba haihuwa ba sai jigila take yi da mu da yaranmu ga shekaru jiki da jini don ma jikin ya horu da aiki ni dai sai nace tunda nake da ita ban ta'ba ganin ta kwanta ciwo mai tsanani ba hana karya lokacin da muke kano ba ta jima da zuwa ba ta ta'ba wani ciwon kai wanda ya d'auketa tsayin kwana uku a kwance tunda na kaita asibiti aka duba ta da maganguna ta warware daga lokacin ban sake jin ta ce mini ba ta da lafiya ba.

Paid book ne wannan littafin kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na ce kawai ta bar shi idan zan kwanta zan sha tea wannan ba shi da matsala da kaina ma zan hada abina.
Ta amsa da to kafin ta juya domin komawa dakinsu. Hauwa ta fito ganina a falon ni kadai sai ta tsaya tana fad'in." Ni kuwa Amina wanene ya gayawa maigidan Sadiya ta zo?"
Na dube ta a tsanake kafin na furta. Kya tambaye ni Hauwa ko kuwa ni kadai nake rayuwa a gidan kin manta tun daga bakin gate gidan cike yake da masu tsaro saboda kin yi bakuwa sai na kira shi na gaya masa kenan?'
Ta fara dariya irin ta kare kai tana fad'in." Haba Amina ni ban tambayeki domin na fusataki ba ya kira ni ne da fad'a yana cewa mu kula da masu shigowa sai naga tunda na zo gidan nan babu wani d'an uwana da ya ta'ba zuwa sai yanzu Sadiya ai ba bare ba ce 'yar uwata ce da babanta da mahaifina uwa daya uba daya suke."
Na ce.'' Wannan kuma damuwarki ce Hauwa kina so ki gaya mini cewa ni nawa 'yan uwan tarewa suka yi a gidan kenan ko?"

Ta girgiza kanta tana cewa." Na ga kin hasala daga tambaya sai cibi ya zama 'kari Amina ko dama haushina ki ke ji ne ban sani ba ko kuwa zuwan Sadiya ne bai yi miki dadi ba."
Na ce." Me yasa zan ji haushin  Sadiya me  ta yi mini Hauwa wai ke don Allah an gaya miki kowa yana da tsatsar zuciya ne. Bayan Sadiya ki kawo wasu gidan nan su zauna bai dame ni ba Hauwa."
Murmushi ta yi bata sake ce mini komai ba ta nufi kicin. Ina nan zaune ta fito da wasu madaidaitan mazuban abinci ta wuce ni. Tsaki na ja can k'asa na tashi na shige d'akina. Wai tambayata take yi wanene ya gaya masa ta yi bakuwa saboda raninin hankali yadda ya kira ta a waya yana tuhumarta ni ma haka ya kira ni ita dai har yanzu ta'ki zama da ni da zuciya daya.
Can wajan sha d'aya na ji yunwa ta yun'kuro mini tabbacin tea din da na sha ba zai d'auke ni ba.
Na tashi da azama na nufi kicin din fatan doya nake sha'wa wanda ya ji attaruhu.
Daf da zan shiga kicin din na ji kamshin wainar k'wai.
Na ji muryarta tana fad'in." Kina nan da cin dad'i dai Sadiya ba kya gajiya da ciye-ciye tsakani da Allah cikin daren nan kin tashe ni da soya kwai "
Na ji maganar ita Sadiyan  tana fad'in." Laulayi ne ya sanya ni a gaba Hauwa dama ya ya lafiyar kura da kwad'ayi tunda na samu cikin nan yake cin kudi wallahi kullum sai Babansu Haidar ya sayo mini balangu."
Ta ce." Wai ba wani sirri da za ki ba ni ne Sadiya wani lamari ne yake damuna wallahi na rasa yadda zan yi na shawo kan matsalar nan ina cikin damuwa mai tsanani.
Na ji tana cewa." Menene kuma ke dai kullum cikin korafi kike Hauwa yana da kyau don Allah ki yi amfani da shawarwarin da muke ba ki. Na gaya miki ko kin sanya ana yi miki taimako dole sai kin had'a da kissa da addu'a kuma. Sannan na fahimci matar nan ba ta da hayaniya kuma tana da kirki daidai gwargwado don girman Allah ki kwantar da hankalinki ku zauna lafiya da juna."
Ta ja tsaki tana fad'in." Duk ina ko'karin yin haka Sadiya amma ba zan boye miki ba wallahi ina tsananin kishin amina. Tabbas abinda ki ka fada a kanta gaskiya ne macace mai kirki da kawaici kuma bata da mugunta ko kad'an wallahi duk lokacin da ta lura na yi fad'a da maigidan ta dinga kokari sasanta mu kenan amma duk da wannan abin da take yi ba na jin zuciyata za ta daina jin zafinta dalilin yadda maigidan ke nuna mini cewa ya fi sonta wannan zahiri ne na tabbatar da haka yana mutuwar sonta ko alwashi ya ci akan abu idan ta yi magana sai ki ga ya sassauta. Sai abu na biyu yau watana kusan hud'u da dawowa gidan nan har yanzu bai yi auratayya da ni ba. yana dai yi mini magana har na kai masa abinci ya ci amma zamu kwana d'aki daya baya kallona duk yadda na kai wajen janyo hankalinsa wallahi ba ya sauraranta Sadiya abin yana yi mini ciwo sosai na kai kaina wurinsa ya fi a kirga na yi shigar da zata sanya ya ji sha'awata amma ko gezau ba ma ya kallona balle na sanya a raina zan rinjaye shi. Abinda yake ta damuna ganin ta samu ciki ni kuma ina so na fita yawan 'ya'ya a gidan nan Wallahi....✍
*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: https://chat.whatsapp.com/HmWvZBqszkCFRsRaL0UYUZ
*PAID BOOK VIP 2K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA 1k VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*141*
Sai na ji tana fad'in." Ai kin fita yawan 'ya'ya Hauwa maza biyu fa da mace daya mu kaddara yanzu mutuwa ta riskeshi cikin kashi uku na dukiyarsa ke ki ke da kashi biyu ita da mahaifiyarsa su d'auki kashi d'aya to menene abin damuwa nan".
Ta ce." Duk da haka dai Sadiya hankalina ya'ki kwanciya wallahi tunda na ganta da ciki nake sha'awar ni ma na samu haka kawai zuciyata ta ki nutsuwa duk yadda na ke ko'karin ganin na danni zuciyata akan abinda take bijiro mini wallahi na kasa Sadiya babban kalubalan da yake damun zuciyata k'aurace mini da ya yi a shimfida ya kuma yi alkawari kan cewa ba zai sake kusantata ba balle na d'auki ciki na haihu. Kin ga kuwa idan ban tashi na nemi mafita ba ina ji ina gani nata yaran za su wuce nawa."
Ta d'an yi jim kafin na ji tana fad'in." Ba zan b'oye miki ba Hauwa abokiyar zamanki ta fi ki kyawun gani tana da jiki mai kyau da diri ta ko'ina kuma mafiakasari mazan yanzu ba kasafai suke son ramammun mata ba. Ki dube ki don Allah kin yi zama 'yar fiyau ya kamata a ce kin yi ko'karin ganin kin fi haka murmurewa komad'ar jikinki ta dawo yadda zai dinga sha'awarki har ya mata da alkawarin da ya d'auka na daina kusantarki."
A raunane ina jin lokacin da ta ce." Da kamar wuya Sadiya duk yadda zan zama wallahi ba ni ce a zuciyarsa ba Amina ce ya fad'i ya sake fad'i baya jin nauyi da kunyata haka yake gaya mini ya ba zan ji haushinta ba abu ne mai wahala na iya cire ganin k'yashi a kanta tunda an fifita ta a kaina ko yanzu da nake yi miki wannan maganar wallahi a buk'ace nake irin ta dabi'a amma haka zan ta dannewa wannan kaydai ya isa ya jefa rayuwata cikin garari tunda ban san yadda zan yi na kawar da buk'atar ba."
Ta ce." Akwai zalinci da cutarwa amma na d'an fara zargi anya ba farra'ku aka yi muku ke da shi ba. Ina ce ai ya san zunubi ne mai girma yak d'aukarwar kansa idan yana hayyacinsa a ganina ba zai aikata hakan ba lallai akwai dalili wata kila an dasa masa kyamarki a zuciyarsa"
Ta ce." Ba na tsammanin haka Sadiya ai na gaya miki hujjarsa ta k'aurace mini saboda na ajiye Sultan yana jinjiri na tafi gidanmu shine dalili wai ba zai sake kwanciya da ni ba."
Ta ce." To shawara ta karshe da zan baki shine ki gayawa mahaifiyarsa domin kuwa akwai k'wara da cutarwa gaskiya idan abin ya yi yawa kina iya shiga wani yanayi wanda ba ma fatan hakan."
Shiru ya biyo bayan maganar Sadiyan ban ji Hauwa ta sake wata maganar ba. A hankali jikina babu kuzari na koma d'aki na zauna tare da nazari da tunanin maganganun da na ji suna tattaunawa.

A lallai ban ga lefin Hauwa ba don ta tsananta kiyayyarta a kaina dama akan ce idan ka ga gida ya gyaru daga maigida ne idan ka ga zaman lafiya ga kishiyoyi to an samu foundation daga wanda ya assasa zaman. Sau nawa ake yin irin wannan auran nasu na hadin iyaye a samu daidaito da zaman lafiya kuma a tara zuria. Na ji daga bakunan mutane da yawa cewa k'iyayyar namiji ta fi ta mace amma ban ta'ba tsammin 'kin da yake yi wa Hauwa ya kai haka ba. Babu wata mace da za ta iya jure wannan cin mutunci da zarafi ya dinga dubar tsabar idonta yana gaya mata ba na son ki ga wadda nake so.
Maganar k'auracewa a shimfida shima babban jidali ne mai girma wanda waliyyai ka iya shigowa ciki. Mai yasa lokacin da ya yi mini irin haka na kasa hakuri ni ma abinda ciwo sosai kuma ta yi hakuri da shi tana kuma son zama dashi duk da a cikin maganganunta akwai wad'anda na d'ora ayar tambaya a kai amma me duk abinda yake wanzuwa a yanzu da sanya hannunsa idan Hauwa kishi da bakincin fifikon da nake samu a wajensa fiye da ita ya d'ebeta ta yi mini wata illar kamar yadda muke ji ko mu gani social media yana da kamasho tunda ya bi son rai wajen gina gidansa kuma ya take mata ha'kkinta na aure. Hauwa ko bata fad'a ba nasan ba ta sona a zuciyarta kawai tana ko'karin dannewa ne abin ya 'kara tsamari da tsanani sakamakon yadda d'aukakata ta dusashe ta ta a wajensa
A tak'aice dai da yunwa ta na kwana a daran sakamakon nazari da tunanin al'amarin da suke faruwa.
Da wuri na fito na samu su Baba Tabawa a kicin sun soya fanke da
kunun gyad'a ya yi kyau da haske na ji dad'i kuwa muka gaisa kafin na d'ebi daidai cikina na fita.
Ina karyawa suka shigo tare ita Sadiyar cikin shirin tafiya muka gaisa da sakin fuska tana fad'in tafiya za ta yi a takaice na furta." To Allah Ya kiyaye a gaishe da mutane gida.
Suka fita tare Hauwa ba ta ce mini komai ba tun bayan gaisuwar da muka yi kana kallonta za ka karanci damuwa a tare da ita.
A zahiri a kwai buk'atar zama a tsakaninsa da ita amma yanayin yadda take nuna mini bakin 'kyashi da kishi ya sanya na yi alkawarin cire hannuna a lamarinta. Ya kuma zame mini dole na kara yin nesa da ita dalilin gudun abinda ka iya zuwa ya dawo tunda mugun nufi ne fal a zuciyarta game da ni.

Na kudi ne littafin nan kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Yammacin litinin ya dawo kamar yadda ya gaya mini da muka yi waya shekaran jiya daga d'akina ya fita ranar da zai tafi don haka ina yi masa sannu da zuwa na sau'ko k'asa. Ita kuma ta hau ba ta sauko ba sai gefin magriba shi ma ya sauko da shirin massalaci sai da ya dawo tukkuna ya zauna a falon yaran suka taru a wajensa yana ta wasa da su. Ka'ida ne idan yana falon masu aikin basa fitowa sai ya kasance ni da Hauwa ne kadai a zaune da yaran ana ta wasa da dariya. Hauwa ta ci ado da jins da 'yar k'aramar riga sai ta yafe wani bakin mayafi a kanta. Wallahi tausayi ta ba ni ainun ganin wanda ta yi wa kwalliyar ba ya yi mata irin kallon k'aunar yake yi

mini. Yana dai amsa mata magana idan ta yi amma ban hangi wani shau'ki da jin dad'in kin burgeni ba abinda yake yi mata ya sanya ni jin kunya da nauyi ta tashi ta shiga d'akinta ya kai sau uku ta fito ta zauna amma ban ce ya san abinda take yi ba.
Ya dube ni yana fad'in." Yarinyar nan Hajara ta sake ba ni sa'ko wajenki yana mota."
Jin haka ya sanya Hauwa yin kicin-kicin da fuska domin yanayin yadda yake sako ni a maganarsa ya fara bata haushi gashi kuma ta ji an ce an bada sa'ko a kawo mini."
Na furta.'' Aikuwa na gode sosai a sanya a kawo nasan abin motsa baki ne."
Na fadi hakane domin ko menene a bud'e shi a gabanta kada ta zargi wani abin tunda ita dabi'arta ce."
Ya d'auki wayarsa kuwa da sauri ya kira Sukairaju ya ce ya duba cikin mota zai ga wata leda mai zane-zane ya d'auko masa ita.
Muna zaune kafin Sukairaju ya shigo ya miko mini wayarsa yana fad'in." Duba gidan Malam D'aha  an fara aiki."
Na kar'ba da sauri da fara'a ina fadin." Alhamdulillahi na fara dubawa an rushe gidan gabad'aya aiki ma ya fara nisa.
Na mik'a mata wayar ina fad'in." Gidan Malam D'aha ne za a sabunta shi."
Ta kar'ba da d'an murmushi irin na saman lebe tana dubawa na dube shi ina cewa." To suna ina yanzu?"
Ya ce." Na sanya su a wani gidan daga zarar an kammala aikin an gyara musu ko'ina za su koma."
Na ce." Na yi musu murna sosai Allah ya saka maka da alheri."
Ya amsa da Amin a takaice."
A maimakon ta miko mini wayar kamar yadda na bata sai ta tashi tsam! ta nufe shi da wayar a hannunta. Na bita da kallo cike da mamaki da tausayi da dariya wai ita dole sai ya ga kwalliyar k'ananun kayan da ta yi.
Koda ta bashi wayar sai ta zauna a gefansa tana dan janyo hannun Sultan da yake kusa dashi a tsaye ya dafa gwiwarsa yana dabo (ta-ta-ta) Ya kuwa fad'i timm! ya tsalla kuka da kar'fi tunda daman sai da ya dafa kujera ya tashi.
Aikuwa ya juya yana kallonta da harara yana ce wa." Menene haka? kina zaune can kin zo kin sanya yaro kuka yarinya ce ke?"
Ba ta ce masa komai ba ta d'auki yaron domin rarrashinsa ya dinga zille-zille yana kuka shi kuma sai tsaki yake ja tabbacin haushinta yake ji dangane da kukan yaron
tana jijjigashi ya'ki yin shiru sai ta dubi Khalil cikin muzanta da jin kunyar abinda yake yi mata ta ce." Kira Baba Tabawa ta zo ta d'auke shi."
Ya furta" D'auke shi kai maza kai mata shi ta goya shi."
Ya d'auke shi da sauri tare da nufar d'akin su Baba Tabawa da shi yana ihu shima yana son kasancewa da uban da 'yan uwansa.
Sukairaju ya shigo da leda mai zane-zane a hannunsa. Mu ka gaisa cikin mutuntawa na ce." Ni za ka bawa ai."
Ya miko mini ledar yana murmushi ya juya ya fita. Ko da na bud'e sai na ga dangin su goruba ne da kad'anya gauta da yalo da d'ata har da alawar madara a cikin wata farar Leda.

Ina dariya na daga kaina na kalleshi tare da cewa." Yarinyar nan ta iya bada sa'ko fa."
Bai ce komai ba hankalinsa na kan k'aramar wayarsa. Minal ta zo tana le'ka kanta cikin ledar "Mama menene?'' tana fad'a tana k'ara zura kanta ciki. Na ce" Zo mu je kicin a wanke kayan dadi ne."
Ta kuwa biyo ni da saurinta twins suna zaune da wayarsa a hannunsa game ya kamo musu.
Na cire ledar alawar madarar na jika musu gorubar domin ba za su iya cinta a bushe ba. Abu ne da ba su saba dashi ba sosai sai ya zame musu kamar nama. Yalo da d'ata da kad'anya duka na gyara musu suka kewaye ni muna ci  Hauwa ta ce ba ta yi sha'awa ba wanda na tabbatar da cewa ta fadi hakane kawai saboda zuciyata tana yi mata zafi babu wata maccan da ko babu uzuri na juna biyu ta ce bata marmarin irin wad'annan kayan gonar. Ganin yadda muke ci da yaran ya ce shi ma a bashi daya.
Usai ta d'auki yalo 'kato ta kai masa.
Ta d'auki wani ta tafi wajan Hauwa tana mika mata. Ta kar'ba amma sai ta ajiye shi saman cinyata ta yi shiru duk ta yi sanyi abin gwanin ban haushi da tausayi domin dai Hauwa ko kana jin tausayinta idan ta kuntuka maka wani takaicin  sai ka ji kamar ka rufe ta da duka saboda haushi.....

Daga karshe ma sai kawai ta tashi ta shiga d'akinta ina hankalce da shi bai bita da kallo ba balle ya shiga damuwa don ta bar wajen.
Ta gama kwanaki biyunta ban san wainar da suke toyawa ba. Na kar'bi girki na kasance cikin walwala da farinciki kamar yadda shima ya kasance duk wata hanyar da zata kara mini mutunci da soyayya ita nake bi a yanzu muddin bai shigo mini da son zuciya ba kalau muke zaune a yanzu kuma idan zai nemi ni sau nawa ba na nuna gajiyawata jikina ya horu kwarai da dabi'arsa sai aka yi katari da wannan cikin da nake d'auke shi ba mai k'yamatar lamarin ba ne.
Na kwana biyu ban ji daga Sahura ba ina jin tun bayan wayar da muka yi take gaya mini Idiris ya buge kwado ya shiga gidanta babu yawunta sau biyu muka kara yin waya kuma idan na soko mata da maganar abinda yake faruwa a tsakaninsu ba ta saurarata fadi take yi ta daina gaya mini matsalarta tunda ni ma goyon bayansa na ke yi.
Katsam yau ta kira ni tana gaya mini tana zargin fa auran da Idiris ya k'ara ya gurgud'e. Na tambayeta dalili ta ce mini kullum a gidanta yake kwana tsayin sati uku kenan kuma neman shiri yake yi da ita.
Jikina ya yi sanyi sosai Idiris bai shirya ri'ke musu yarinya ba ya aura aure duka bai fi wata hud'u ba an fara cin karo da matsala. Ta ce mini ai tana zargin ma yarinyar tana da juna biyu  ta ji Yayarsu wato uwar mijin Yusura tana fad'a a wata had'uwa da suka yi a gidan sunan k'aninsu amma dai ba su fito sun fad'a mata cewa sun rabu ba ta ji dai suna fad'in saura amaryar Idiris a jerin masu haihuwa domin itama  ciki ne da ita.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*142*
Na cika da mamaki 'kwarai da gaske da jin wannan lamari
ni babban takaicina ma yadda yake ko'karin mayar musu da yarinya k'aramar bazawara tunda a yadda take ba ni labari duka bata fi shekara ashirin ba idan hakane kuwa ai da kadan ta girmi Yusura. shari'ar aure ba a yanke ta kai tsaye amma jikina yana ba ni cewa matsalar daga wajansa take wanda itama Sahura take zargin hakan domin ta ce har yanzu ya'ki yi mata bayanin komai sai kame-kame ya yi da kuma neman shiri da ita to kuwa duk yadda ya kai ga b'oyewa dole watarana kowa ya ji dalili mussaman a nasa b'angaran tunda har tana da juna biyu Allah kyauta ya kuma rufa asiri shine kawai abinda za a ce.
Kwana bakwai da dawowarsa guda yake gaya mini na shirya satin da za mu shiga juma'a kenan za mu je jigawa d'aurin auran Alhaji Sulaiman mijinsu Hajiya Aziza. Idan an daura za mu kwana d'aya sai mu dawo gida. Na ce masa to shikkenan, cikin zuciyata ina ta mamaki ashe auran da na ji kwanaki yana fad'a da gaske ne. Kuma wata'kila budurwar zai aura lallai tsufa ya yi gardama an kuma shigo da son zuciya iyayen yara da su kansu masu auran yara k'ananu. To Ashe tana jika a cikin gidana ni ma. Ni dai bayan dawowarmu daga d'aurin auran Alhaji Sulaiman kamar yadda ya fad'a sai nake ganinsa wani sukuku babu irin sa'ke-sa'ken da zuciyata ba ta yi mini ba akan ganin ya canza na d'an ta'kin lokaci. Zuciyata na kawo mini ko shima ya yi sha'awar budurci ne tunda mafiakasarinsu abinda sukewa kulafuci kenan ya sanya suke ture kunya da kawaici su auro 'ya'yan cikinsu su kwanta gado daya da su.
Na zura masa ido kawai yanayin yadda ya fara tafiyar da al'amuransa na rashin walwala da yin shiru da nazari ni ma sai na tsiri yin hakan muka cigaba da tafiya a haka bai gaya mini damuwarsa ba ni ma ban nemi da na ji ba. A d'ayan biyu ne ko matsalar kasuwanci ko kuma shi ma auran yake nema amma kuma yana cike da zullumi da damuwa ga yawan kallona da yake yi daga zarar mun had'a ido sai ya wayance ya tsiri yin wani abin. Yanayin da ya 'kir'kirarwa kansa bai hana shi yin mu'amula da ni a duk lokacin kwanan aurena ba. Hauwa dai har yanzu jiya iyau domin ga dukkanin alamu cutar damuwa(Depression )ddaf take da ta kamata abin gwanin ban tausayi da takaici.
Ana haka Sahura ta kira ni take gaya mini Idiris suna kotu da amarya iyayanta sun buk'aci ya saketa ya ce sai an biya shi abinda ya kashe kafin auranta.
Alkali da ya nemi jin dalili kaf aka gaya masa. Duk wata hidima ta gida ya gaza sai masifar kwanciya da yake yi da yarinyar mutane babu dare babu rana ga rashin k'oshi tunda ya yi na amarci ya jingine k'aramin buhun shinkafa da rabin kwalin taliya da makaroni da kwalbar manja da mangyad'a da had'in maggi. Da suka 'kare sai ya shiga auno mata wake yace ta dinga

yi fate-fate yana 'kara jini tunda tana da juna biyu sai ta fi sati daya tana cin wake fate ko 'kulu da mai da yaji da safe ya sayo mata kunnu da awara. Yadda yarinyar take fad'a tana kuka sai ya shigo da leda cike da abin dadi ya zauna ya ci a gabanta ya bar ta da tsotse 'kashin da ya sale masa tsoka. Ya kuma isheta da bala'in kwanciya da daddare ga rashin abinci mai kyau. Da ta ce ta gaji da cin wake sai ya auno mata tsakin masara mai yawa da barkono da farin maggi da manja wai ta dinga yin d'anmalale.
Yarinya mai garin jiki duk ta tsotse gashi baya dawowa da wuri sai sha biyu na dare wataran har da rabi tukkuna zai sanya mukkuli ya bud'eta tunda idan zai fita kulleta yake yi ta ciki
yau da gobe ta'ki wasa har dai iyayenta suka gane wuya yake bata yaran shago ma suka bada shedar kulleta yake yi kuma wataran akan idonsu yake dawowa tunda suma suna kaiwa sha biyu na dare ba su tashi daga aiki ba.
Sosai na tausayawa yarinyar. Ita kuma Sahura sai na lura kamar murna take yi tana fad'in hakkinta ne domin duk auran da aka gina shi akan zalinci da kwadayi k'arshensa kenan wallahi ba zata rike masa d'an ko wace shegiya ba.
Na ce." Ke abinda yake damunki kenan ko Sahura an ce mijinki yana raba dare a waje shi ba wani business yake yi ba na cin kasuwar dare ba balle a ce ba ki yi tunanin wani abu ba?"
Ta ce." Ba zai wuce yana yawon neman mata da d'an kudin da ya samu ba, ai ki bar d'an iskan namiji Amina kin ga ni ban ci ba haka zalika yarinyar mutane ma da ya auro bata ci ba ya tafi yana kaiwa matan banza shiyasa tunda ya yi auran nan kamar na sani ban sake ba shi kaina ba."
Na ce." Lallai akwai buk'atar ki sanya ido akan Idiris Sahura kada kishi ya sanya nan gaba ki yi nadama idan ya kasance Idiris ya fad'a harkar bariki kina da kamasho tunda ke kin San wanene shi gashi kina ba ni labarin irin durzar da yake wa yarinyar mutane yanzu da babu ita ai zai sake tsunduma tunda ke kin daina ba shi kanki. Haihuwar da ta ratsa tsakaninku ta wuce komai."
Ta ce." Haka kowa yake cewa Amina amma bari kiji wallahi yadda Idiris ya cire kawaici a kaina ya gwada mini rashin Imani babu wani dalili da zai sanya ni don ya shiga matsala a yanzu na damu. Na gaya miki fa yanzu ko ya sake ni ba ni da damuwa Allah ya yi mini rufin asiri ina da matsuguni da 'yan kudi a asusuna zawarci zan buga mai kasafiti Hajiya."
Dariya ta kama ni na ce." Sahura ki dai yi tunani akan maganata ki yi hakuri ku samu daidaito don Allah ko saboda yaranmu babu dad'i Idiris ya lalace dole za a danganshi dake ace tsohon mijinki ne kuma uban yaranki.
Ta furta." Ai ko zamu daidaita ba dai yanzu ba Amina wallahi yadda ya gumami ni ba'kinciki in sha Allahu masifar da zai tsinci kansa sai ta shige wadda ya jefa ni."
Da haka muka yi sallama tunda duk ta inda na biyo sai ta doje ta nuna yanzu ba lokacin da ya dace a ce ta tausaya masa ba ne.

A daran ranar da muka yi wannan tattaunwar da Sahura bayan isha'i muna falon gabad'aya masu aiki da yaran ban da Hauwa da yake girkinta ne tana

ta kai wa da kawowa daga kasa zuwa sama. Na ce da Baba Tabawa ta kawo mini abinci. Towon shinkafa suka yi miyar taushe da tantakwashi. Sun jima ba su miyar taushe a gidan ba wannan dalilin ya sanya mini mugun mararin son cin towon.  Ina ci muna hira da su jefi-jefi Hauwa ta sakko kai tsaye dakinta ta nufa sai ta d'an tsaya tana kallona kafin ta ce." Maigidan fa baya jin dad'i Amina."
Gabana ya buga da k'arfi a take a lokacin na ji abincin ya fitar mini daga rai Allah ma dai ya sa na ci da yawa. Na daidaita yanayina sosai kafin na ce." Mai yake damunsa?"
Ta d'an ta'be bakinta tana fad'in." Ciwon kai na ji yana gayawa likitansa yanzu tun rana da shi dai ya yini na yanzu ya yi tsanani ko 'daga kansa baya iya yi yana kwance."
Na yi 'kasa da kaina abin har ya kai ga kwanciya irin haka wace irin matsala ce take damunsa da har zai ajiyeta a ransa ta haddasa masa ciwo.
Ta shige dakinta ba ta sake yi wata magana ba.
Kafin na haura saman sai da na sanyo hijabi jin cewa likitansa yana kan hanya
Yana kwance shar'be a gado ya dafe kansa da hannunsa.
Na zauna gefansa jiki a mace ina fad'in." Baba baka da lafiya ashe?"
Ya dube ni da gefan ido ya furta." Ciwon kai ne Amina yanzu nan ya sake tsananta."
Na ce." Kana jin sa ashe a hankali a hankali ba ka yi magana ba sai yanzu da ya kwantar da kai an ta'ba wasa da lafiya ashe."
Ya yi shiru bai ce komai ba. Na gyad'a kaina ina fad'in." Ni ba yarinya ba ce duk yanayin da kake ciki ina hankalce ban buk'aci dole ka gaya mini sirrinka ba wata'kila baka son kowa ya sani shiyasa ka yi shiru abin yana cin ranka ya kamata a ce ka sassautawa kanka dalilin gudun faruwar mummunar abu akwai shekaran girma a tare dake kuma idan ban manta ba kana da hawan jini bai kamata a ce ka dinga ajiye wani abu a cikin ranka ba. Amma ina so na gaya maka cewa ko ka fad'a ko baka fad'a lallai kana cikin damuwa domin gabad'aya al'amuranka sun canza a tsukin lokacin nan."
Ya yun'kura ya tashi zaune yana kallona da wani irin yanayi ya ce." Lallai ina cikin damuwa Amina amma ban san yadda zan yi na fitar da kaina daga cikinta ba."
Na ce." Duk abinda ya yi tsanani ai maganinsa Allah kaine ka ke da hanyar fitar da kanka daga cikinta idan ka sanya hakan a ranka."
Ya gyad'a kansa yana kallona amma bai ce komai ba.
Jikina ya sake yin sanyi na d'an riko hannuna a hankali na ce." Idan babu takurawa ka gaya mini damuwar da take damunka ko Allah zai sanya ina da shawarar da zan baka."

na kudi ne wànnan littafin Yar uwa don Allah a duk inda za ki gan shi kada ki karanta sai kin biya ni hakkina.

Ya furta." Malam 'Daha ne ya ba ni 'yarsa amma ban san ko wacece daga ciki ba, kin san dai gidansa cike yake da yara ko?''

Kunnena ne ya yi dumm! kamar irin kumfar sabulu ta shiga ciki na ji ya sake rintse hannuna yana fad'in." Ban zan iya bijire masa ba Amina wallahil-azim ba zan 'ki 'karbar tayinsa ba."

Na zuba masa ido kawai ina kallo bakina ya yi nauyi na rasa ma abinda zan ce saboda zahiri na 'kadu da jin maganar nan gidan Malam D'aha babu wata cikakkiyar budurwa duk matasa ne kuma mafi akasari daga sassan gidan suke fitowa alamu sun nuna wasu daga ciki 'ya'yan yaransa ne irinsu malam Rabi'u. Jikokinsa kenan

Hajara ita ce kadai 'yar budurwar da ta fara tasawa tunda ta fara 'kirgar dangi sun yi cibir-cibir a cikin riga ba ma su kai a sanya musu rigar mama ba. Na daure na ce." Ai duk babu wata budurwa cikakkiya a gidan Malam D'aha." Ya ce." Akwai uku da bai aurar da su ba sauran jikokinsa ne a cikin ukun ya ba ni d'aya ban santa ba ni ma."

"Hajara ce abinda zuciyata take raya mini kenan. Muka yi shiru ni dashi muna duban juna Hauwa ta shigo sanye da hijabi a jikinta ta same mu a haka mun k'urawa juna ido ga hannuwanmu a ri'ke

ta kasa jurewa muryarta tana rawa ta ce." Ka ce baka da lafiya maganar duniya na yi maka baka tanka mini ba kana kwance kana jina yanzu gashi kuma yanzu na shigo na gan ku ma'kale da juna wallahi Amina ku ji tsoron Allah hakkina ba zai bar ku ba ba zan ta'ba sahale muku ba a ranar lahira."

Na juya da mataccen jiki ina kallonta. Wata gaud'iya da ita ana ga gabas tana ga yamma. Karamin tsaki kawai na ja ban ce komai ba na cire hannuna daga cikin nasa. Ya sake kamowa yana fad'in." Kin ce akwai shawarar da za ki ba ni ko Amina wallahi ba ni son auran da ake ko'karin ma'kala mini abinda yake zuciyata na gaya miki tunda kin matsanta ki ji kada ki d'auki maganata a matsayin dad'in baki a yanzu dai babu ajandar aure a tare budurwa ko bazawara kin san matsayin Malam D'aha a wajen mahaifina da ni kaina da irin gudumuwar da ya ba ni a rayuwa abu ne mai wahala na yi ja'in'ja akan wannan umarin nasa Amina

ba ni da mafita ne dole na gaya muku halin da ake ciki daga yau zuwa ko wane lokaci za ku iya jin labarin d'aurin aurena domin gidan Malam D'aha ba'a bida'a idan an d'aura aure yarinyar zan je kawai na d'auko."

Abin ya daki Hauwa k'warai da aniya ta zuba masa ido cikin k'aduwa tana fad'in." Aure da gaske za ka yi to kai yaro ne da za ka ce an ma'kala maka daman can kana so akwai wanda ya isa ya yi maka dole ne? ashe kana da lafiya ta mazantaka da kuzari irin na maza tunda har zaka iya 'karbar auran budurwa 'kan'kanuwar yarinya.

Ya 'kankance ido yana fad'in." Ba ni son hauka da rashin hankali Hauwa ki kiyaye ni wallahi kada ki sake ki fusata ni."

Ta ja tsaki ba ta sake cewa komai ba ta kad'a kanta ta kama hanyar fita.

Ya ja tsaki tare da sake juyowa gare ni yana fad'in." Ya za mu yi ne Amina ta ina kike ganin zan warware wannan mas'alar da na shiga.

Ajiyar zuciya na sauke a nutse na furta." To ai ni ban isa na hana umarinin Ubangiji ba. Na d'auka wata matsalar ce ta daban shiyasa ka ji na ce maka ka gaya mini zan baka shawara. Lamarin aure kuma ai yin Allah ne Amina bata da hurumi anan sai addu'a da fatan alheri."

Ya ri'ke hannuna sosai yana fad'in. " Kin amince a yi? kina ganin babu komai idan an yi din?"
Na gyara kaina gabana na dokawa na ce." Idan ma da matsala ai ban isa na sani ba tunda ni hallitar Allah ce a karan kaina ban san abinda zai same ni daga yanzu zuwa gobe ba kaga kuwa ba ni da abinda zan ce anan kamar yadda na fad'a da farko Allah Ya sanya alheri yasa abokiyar arzikinka ce. Wannan shine kawai addu'ar da zan yi."
Ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta.'' Ban za ci zan samu ha'din kanki cikin d'an'kankanin lokaci ba Amina. Lallai na yi sa'ar samun mace tagari mai ko'karin ganin ta samar mini da nutsuwa cikin kowane yanayi na gode sosai Allah Ya yi miki albarka."
A tak'aice na amsa da amin ina ta kallonsa ganin ya wartsake idan ma da ciwon kan to a kashi dari hamsin ya sauka sai abinda ba za a rasa ba.
A haka likitansa ya zo ya dudduba shi yana fad'in jininsa ya hau kad'an shine kuma ya haddasa masa tsananin ciwon kai da jirin da yake ji ya zama dole ya daina tsanantawa kansa damuwa.
Ya tashi ya fita minti talatin a tsakani ya dawo da magunguña a leda ya yi bayanin yadda ya kamata a ce an yi amfani da su daga yanzu. Ban sauka ba sai da na tabbatar da cewar ya ci abinci sosai sannan ya sha maganin a gabana tukkuna na yi masa sallama na sauka gwiwata kamar an rad'e da gora saboda mugun sanyin da jikina ya yi jin wannan batu......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124.....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*143*
Ni jin wannan batu gabad'aya ya kassara mini dukkanin karsashin jikina. Na yi shiru zuciyata na harbawa tare da tariyo maganganunsa akan auran da yake yi wa lak'abi dana cushe. Ba ni fargabar ya yi aure a gidan nan saboda na riga na san matsayina a zuciyarsa idan ma yana amfani da kalaman yaudare wajen nuna mini soyayya tabbas to akwaita a zuciyarsa ko da kuwa da akwai matsugunin wata. Matsalar dai anan 'kankanuwar yarinyar da zai auro ya kawota cikinmu shine tashin hankali tun lokacin da yake gaya mini zuciyata take hasaso mini Hajara ce domin kaf yaran da suke gidan Malam D'aha itace a samansu ba su kaita girma ba ita zamu kira da budurwa amma a rashinta domin yadda take a tsamure a tsuke sai uban tsayi bana tsammanin ta fara jinin al'ada.
Lallai wannan babban lamari ne da ya tunkaro mu gabad'aya domin idan har Allah Ya kaddara auran nan to sai da ya rainin yarinyar nan duk da matarsa ce ba zan yarda ya haye musu kan d'iya ta had'u da lalaruba. Malamai suna ta wa'azi kan cewa iyaye su daina irin wannan auran na cutarwa to da haka za mu kira shi ma a wannan zamanin domin dai muddin a fake da cewa sunnar manzon rahama ce yin haka to akan jefe yara cikin halin damuwa a gaba. Dalili zamanin Annabi Muhammadu S.a.w daban yake da wanda muke

ciki a yanzu idan an fake da cewa za a yi koyi da shi akan abinda ya wanzar lokacin zamaninsa ana samun matsala dalili shi daban yake cikin duk wata hallita. Kai tsaye a yanzu ba zan zargi Malam D'aha da cewa shima kwad'ayin dukiya ne ya sanya shi daukar yarsa 'karama irin wannan ya bawa tsoho wanda idan da ya yi aure da wuri babu shakka ya kusa jika da ita domin dai Hajara ta wuce a ce 'yarsa idan auransa na fari ya d'ore duk da lokacin ma sai da ya zama tuzuru ya yi  ya kuma fara da mace to ba ba shakka Hajara sai dai ta zo a jikanyarsa ta farko. Fisabillahi Malam D'aha bai dubawa yarinyar nan ba kuma ya tauye mata rayuwa ko da Alhaji Sulaiman ya yi aure eh tabbas budurwa ce amma wadda ta jima bata auru ba domin na ga calendar su shi da ita ta girmi Hajara sosai a k'alla ita za ta yi irin ashirin da biyar zuwa da bakwai. To idan ya zame masa dole auran budurwar sai ya nemi mai k'wari ba irin Hajara ba wadda yanzu ne take tasowa ba tasan ma menene auran ba. Na yi zaman sati daya a gidan na kuma fahimci cewa gidan na da tarbiya masu wadatar zucci da malunta ina ganin saboda kwad'ayin dukiya ba zai d'auki yarsa ya bayar ba sai don wani dalili nasa ko hango nagarta da tabbacin za a ri'ke masa  'yarsa a kula da ita. Wannan shine abinda na fi gazgatawa daga gare shi ba wai ya bashi ita ba ne domin ganin yana da kudi  da rufin asiri.
Kwanan tunani da zullumi na yi kan wannan lamari gabad'aya kaina ya d'aure na rasa yadda zan yi na auna mas'alar a sikeli domin hango cancanta da dacewa.
Ina fitowa daga wanka kira ya shigo wayata dake ajiye a gefan gado na kàrasa da sauri na d'auka. Baban Saude ne gabana ya yanke ya fadi domin ban kawo komai ba sai mutuwa. Shikkenan Dada ta rasu ban je na dubata ba Allah ya raba ganawarmu.
Hannuna na rawa na sanya wayar a kunnena cikin mutuwar jiki da saranda na yi sallama. Ya amsa da dakakkiyar muryarsa wadda hakan bai zame mini abin mamaki ba tunda sanin da na yi masa mutum ne tsayayye ba komai ne yake gigitashi ba ko da kuwa mutuwar ce.
Murya na rawa na gaishe shi ya amsa a dakile kafin ya rufe ni da fad'a ta inda yake shiga ba tanan yake fita. Na yi kasa'ke da waya a kunnena ina sauraransa domin dai abinda ya tsana kenan yana magana a katse shi shiyasa na bari sai da ya tsahirta tukkuna gabana na dokawa na furta." Baban Saude Hauwa sharri ta yi mini wallahi tallahi ina ko'karin ganin na kiyaye shiga hakkinta wallahi Allah d'aya kenan ban san abinda yake tsakaninta da mijinta ba. Bana ta'ba yarda ranar girkinta na 'kebe dashi na tsayin lokaci ko jiya ma ita ta gaya mini bashi da lafiya na hau domin duba shi kuma babu abinda ta same mu muna yi a zaune kawai ta same mu."
Ya furta." Na dai gaya miki ki kula idan har don kina ganin kin fi ta fada a wajensa kuke had'e mata kai har ku dinga shiga hakkinta ki daina domin ba ni so a ce ranar lahira kun tsaya a gaban Ubangiji ana yi muku hisabi yadda ta kira ni tana kuka haikan shine abinda ya daga mini hankali Amina kada ki zalinci duk matan da zai kawo gidanki, ki yi iyakacin bakin kokarinki wajen ganin kin fita hakkin kowa ki kuma nuna masa kuskuran abinda yake aikatawa. Kada don kin samu dama a wajensa ki cutar da wata mu maza ba

mu da tabbas watarana zai iya juyowa kan ki hakkin wad'anda ki ka zalinta ya fara bibiyarki. Ko kin ta'ba jin an ce gaskiyar mutum ta k'are. Idan kina da gaskiya da gudun hakkin wani sai ki ga kin zauna lafiya a duniya domin Allah ba ya shiri da mai zalinci.''
Ya kai k'arshen maganar  da tausawa.
Na ce." In sha Allahu Baban Saude zan kula na gode sosai Allah Ya kara girma."
Ya amsa da "Amin Ya Allah."
Muka yi sallama. Na ajiye wayar ina dubawa. Lallai Hauwa bata da mutunci yau kuma abinda ta shiryo mini kenan.
Kayana kawai na zura zuciyata na tsalle na fita falon shiru ina d'an jiyo maganganun yara a d'akinsu suna shirin makaranta.
Na buga kofar dakinta da d'an karfi na ji tana fadin." Wanene?" Kai tsaye na ce." Ni ce"
Ta d'auki murya bata sake magana ba jim kad'an ta bude tana sanye da kayan bacci cotton riga da wando da hula.
Muka had'a ido ganin yadda fuskata take a murtuke ya sanya itama ta daidaita yanayinta. Na ce." Daga yau sai yau kada jahilar k'wakwalwarki ta yi miki tunanin kiran wayar wani daga cikin alhalina ki kai masa 'karata Hauwa wai shin me na yi miki ne? Ni ce matsalarki ko mijinki Hauwa? me yasa ki ka sanyo ni a gaba ki ke haka kan ki sukuni a kaina me na tsare miki  na fad'a da babban sautin da kowa zai ji na ce.'' Yau sai kin gaya mini abinda na yi miki a gidan nan Hauwa ashe rashin mutuncin na ki har ya kai ki kira Baban Saude ki juya masa magana a kaina ni na yi mini ko mijinki da za ki nemi ki hada ni da iyayena."

Kada ki karanta wannan littafin ba tare da kin biya ba na kudi ne

Babu damuwa a tare da ita ta furta." Abinda ki ka yi mini a bayyane yake Amina tunda kin buk'aci ki sani ai zan gaya miki ko kin zata tsoronki nake ji ne? "
Ta fito falon sosai ta tsaya daf da ni ta cigaba da cewa." Na gaji da wannan kisan mummuk'en da ki ke yi mini a gidan nan, na gaji shiyasa na sanar da Baban Saude tunda na lura shi kad'ai ne yanzu zai gaya miki ki ji kuma ba mazalinci ba ne, kin had'a kai da miji kun ware ni kuna  nuna mini cewa ni ba matar gida ba ce. Kin kanainaye shi da kissa kin hana shi yin mu'amula da ni, me yasa zan yi shiru a kan ki Amina ai ba ki isa ba wallahi dole ne na gayawa magabatanki."
Na ce." Banza shashasha sakarai kawai to kin fad'a kin ji dad'i duk yadda ki ke ganin Baban Saude ya ba ki goyon baya ba zai ta'ba ajiye ni ya d'auke ki ba, gaud'iya kawai wadda ba ta da lissafi."
Ba ta tsammaci wad'annan maganganun daga wajena ba ta tunzura ainun ta fara auno mini zagi manya-manya tana kusanto ni kamar yadda dai ta dinga yi wa Hajiya Maryam. Masu aiki kaf dinsu da yaran suka fito suka tsaya muryarta ce kawai take tashi.

'Yar iska kawai ni za ki kira jahila wanda asali da nasabata ta fi taki. Matsiyaciya na fa san tarihin rayuwar da ki ka gudanar a baya kafin ki yi tsalle ki shigo gidan nan ta karfi da ya ji kin dabaibaye mini miji ta ko'ina. Amina ba tsoronki nake ji ba fa ki ka kara zagin.......Ba ta kai ga kàrasa maganar ba ya d'auke fuskarta da wani lafiyayyan mari. Da yake ita kadai ce ba ta ga sakkowarsa tunda ta juya baya tana kallona tare da nuna ni da yatsa shiyasa ba ta ankara ba amma ni da masu aiki da yaran duka mun ga lokacin da ya sauko a ki'dime domin duk zurfin samansa sai da ya ji shouting dinta.
Ta dafe kuncinta a gigice tana nishi ta juya suka dubi juna ita da shi yanayin fuskarsa ya canza ainun da mugun takaici da b'akinciki.
Ya furta." Kin gani ko? Hauwa idan na ce miki kece matsalar gidan nan ki ji haushi yanzu tsakani da Allah menene haka wace irin sakarai ce ke mara hankali da wayo tsokane mata ido za ki yi ne ko kuwa dukanta za ki yi ba ki duba abinda take d'auke da shi a cikinta a gaban yara kina ta zaginta me ki ke so ki nuna musu?"
Hawaye suka dinga karakaina a kumatunta tana fad'in." Ita ba ka ji zagin da take yi mini ba yanzu ban girmi Amina ba idan lissafi shekaru za a yi me ya sanya don ta zo a Uwargida nake mutuntata daidai gwargwado ita sheda ce har dakinta nake bin ta na gaisheta me yasa za ta kira ni da sakarai shashasha. Kuma na zauna ina kallonta da kai da ita abinda kuke yi mini Ubangiji Allah yi muku fin sa."
Ya furta." Gaisuwar banza da wofi daga yau ki daina gaisheta tunda ba don Allah ki ke yi ba. Duk abinda kuke yi ina hankalce kuma nasan halin kowacce daga cikinku rashin mutunci za ki yi mini a gida abinda nake ji yana faruwa a waje shine ki ke ko'karin wanzar mini da shi a gaban yarana. Dame ki ke so su tashi ko su tasirantu, ke ba za a taba zaman lafiya dake ba ballantana na sanya a raina cewa ko bayan raina za ku had'e mini kan yarana su gaza banbance uwar da ta haife su. Wata matsalar ki ke so ki samar mini da ita a gida ta zage-zage Allah Ya jikan Maryam duka tarbiyar da ta yi musu tare da goyon bayan wad'annan bayin Allan mai inganci ce tunda nake da yaran nan ban ta'ba jin wani ya yi mini zagi a gida ba saboda baki da mutunci ki tsaya gaban  uwarsu kina zaginta akan wane dalili?"
Ta yi shiru tana kuka mai tsuma zuciya domin dai zahiri marin nan da ya taska mata a kumatu ya dakushe duk wani karsashi da 'kumajinta.
Ya dube ni rai a b'ace yana fad'in." Wannan ya zama na farko ya kuma zama na karshe Amina ba zan d'auki wannan shashacin ba. Kada ku kuskura makamacin abinda ya sake faruwa da wannan safiya ya kara kasancewa. Duk abinda ya shiga tsakaninku a same ni a gaya mini na yi hukunci amma ban yarda da irin wannan rashin mutuncin ba a gidana a kuma gaban yara."
Na daure sosai zuciya na 'yar hantsile na ce." In sha Allahu."
Ya juya ya dubi yaran suna sanye da uniform sun yi tsuru-tsuru Khalil na ra'be a gefe yana kuka sauran kuma idonsu ya gwale kamar su rushe da kukan suma. Ya yi wani irin tsaki mai tsayi abinda ba da'biarsa ba ya ce da Mairo su koma ciki da yaran.

Ganin ya bar wajen ya sanya ni ma da gaggawa na shige d'akina na zaune gefen gado kawai sai hawaye suka kwaranyo mini Hauwa ta zame mini annoba. Wai dama haka ake kishi shiyasa ashe ake kashe-kashen juna. Ita Hajiya Maryam na ta kishin na sabauta rayuwa ne a yi mutuwar kasko ban mora ba ke ma ba za ki mora ba. kishin ramuwar gayya da kwantar da mutun har zuwa kushewa.
Lallai ne Hauwa duk ranar da ta samu dama a kaina za ta iya yi mini illah dalili na ji tsoro k'warai da gaske ganin yadda take tsalle da han'koro a kaina kamar za ta kawo mini naushi a hanci a son ranta ma kawai mu gwada 'yar kwanji tunda ta mayar da ni jaka mara lissafi da tsinkaye irinta. Har duniya ta nad'e ba na tsammanin zan yarda na had'a kwanjina dana kishiya.
To wai shin me ta sani a kaina ne da take ta nanata cewa ta san irin rayuwar da na yi a baya? Me na yi mai muni wanda zai janyo mini zind'e da gori a rayuwata.
Na sake goge hawayen da yake sauka a dakalin fuskata. Hauwa ba ta sona yau na sake gazgatawa asalin kishi mai muni take yi a kaina. Kuma ba kowane ya kara rura wutar tsanata a zuciyarta face shi da yake nuna mata 'kiyayya tare da kiran sunana a matsayin matar da ya ratayawa fulawar soyayya a kanta ita da take ganin ta taka tudu biyu matsayin matarsa kuma jininsa.........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700....VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*144*
Ya shigo dakin yana tambayata mai ya had'a mu kai tsaye na ce." Ka je ka tambayata me ta sani a akaina kafin ka shigo ka tuhume ni. Yau ina so a yi ta 'kare a gidan nan lallai ya zama dole Hauwa ta sanar da ni da kai abinda ta ce ta sani a kaina domin yadda ta fad'i hakan to dole ne akwai abinda ta sani din a kaina wanda ta ji a duniya ko kuma a lokacin da kake neman auranta ta gaya mata wani abu kafin ka aure ni. Na ji da kunnena kana gaya mata mace mai irin jikina bata burgeka wa'ala a lokacin giyar soyayya ta sanya ka gaya sanar mata cewa Amina fasika."
Subahanallahi! Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ya dinga nanata wad'annan kalmomin kafin ya zauna a kusa da ni da wani irin sanyin jiki ya riko hannuna na cire ina dubansa idona tsaye na ce." Ba zan saurareka ba a yau har sai Hauwa ta gaya maka abinda ta sani a kaina kafin 'kaddara s
aure ta ratsa tsakaninmu magana ce mai harshen damo ta furta."
Ya yi shiru kansa a kasa tsayin wani lokaci ya dago yana dubana lokacin zuciyata ta gama bushewa 'karyar neman fitina Hauwa take yi yanzu ne asalin rigima ta da ita zai fara.

Ya furta." Ki saurare ni Amina ba ni son damuwa da tashin hankali idan kin duba halin da nake ciki na rashin wadatacciyar lafiya kada zantukan Hauwa su yi tasiri ku daga mini hankali."
Na ce." Kowa cikin lalura yake ni ba ka ganin abinda ka 'kunsa mini ne, ina so ko ba na so na ha'kura ina ta ibada dashi a tare da ni. Na fi ka jinjiki a wannan ga'bar mu cire maganar ciwo ta gaskiya za mu yi wallahil-azimin idan har yau Hauwa ba ta gaya mini abinda ta sani a kaina ba sai ka sake ni."
Ya zura mini idonsa ransa a b'ace ya ce." Me ya kawo maganar saki a cikin maganar da muke yi ke ba ki da hankali Amina?"
"Ba mu da hankali har kai gabad'aya taron mahaukata ne a gidan.
Ya furta." Zagi na za ki yi?"
Na gyad'a kaina ina fad'in." Ni ka zage ni."
Ya yi shiru na d'an wani lokaci kafin ya ce." Ba ki ga hukuncin da na yi mata ba kenan a kan ki ai na ji abinda take fad'a.
Na ce." Wannan damuwarka ce kai da ita ni ina gaya maka cewa ka tashi ka je ka tambayeta abinda ta sani a kaina na abin kunya."
Ya ce." Ba zan tashi ba tunda abinda na yi mata a kan ki bai yi miki ba ki d'auki matakin da ki ke ganin za ki d'auka ba fa tsoronki nake ji ba Amina."
Na ce." Ina ruwana da abinda da ka yi mata ai  ka saba zalintarta. Yau ka fara?"
Shiru ya yi bai dube ni ba tashin hankali ya gama bayyana a tare da shi.
Ya tashi ya fita bai sake cewa komai ba. Ban yi a kasa a gwiwa na bi shi saman sai na same shi kwance ya hard'e hannunsa a k'irji abin duniya ya ishe shi
Na zauna gefansa ya kalleni na kalle shi  na ce" Ka tashi mu yi magana don wallahil-azimin yau sai Hauwa ta gaya mini abinda ta sani a kaina."
Bai tashi ba illa iyaka ido da ya zuba mini yana kallona.
Jim kad'an ya tashi zaune idonsa har yanzu a kaina ya furta." Ni dai ban san komai a kan ki ba face alheri Amina kuma babu wani dalili da zai sanya na zauna ina 'bata ki a gaban Hauwa to na ce me kan ki wannan ba d'abia ta ba ce."
Na ce." Ba zan yarda ba a wannan ga'bar domin da kunnena na ji a shekarun baya kana gaya mata kalmar kaskanci a kaina ba ka son mace mai irin suffata.
Ya furta." Eh da farko ra'ayina kenan amma yanzu na canza ina so dalilin da ya sanya ma kenan ba ni yin wani doki da marmarin wannan yarinyar da aka ba ni bunkure."
Na ce." Da farko kuma ka ce kaima ba kasan yarinyar ba. Anan ma ka sake tabbatar mini da cewa baka jin kunyar 'karya
Ya furta." Kin d'auke ni munafiki kenan?"
Na gyad'a kaina ina kallonsa ido cikin Ido.
Ya ce." Na ji tashi ki je kada ranki ya 'baci.''
Na ce." A shirye nake ai ko kana tsammanin akwai wani b'acin ran da zai dame ni wanda ya danganceka."
Ya yi shiru tare da komawa ya kwanta.

Na cigaba  da sakin maganganu masu zafi har sai da ya fusata ya sake tashi zaune jikinsa na kyarma ya nuna mini hanyar fita.
Na ce." Ba zan fita ba wallahi sai ka kira Hauwa yanzu ta fad'i abinda ta sani a kaina na sharri."
Ya ki'dime sosai yana d'an tari ya ce." Bala'in ki ya kashe ni Amina ko kuma kawai ki sanya fillo ki 'karasa ni ki huta wace irin masifa ce wannan."
Na ce." Ba zan kashe ka ba amma ba zan yi shiru ina kallo ana yi mini abinda bai dace ba.
Ya ja tsaki ya sake komawa ya kwanta na janyo kafarsa daya ya tashi zaune da azama yana kallona da mamaki abinda na yi fuskarsa gabad'aya ta canza da tsoro da fargaba dalili bai hangi nutsuwa da kwanciyar hankali a tare da ni ba."
Ya tashi ya kama hanyar fita babu kuzari.
Mintina biyar suka shigo dakin tare da ita. Har yanzu a hargitse take idonta ya yi luhu-luhu saboda tsabar kuka.
Ya dube ni kafin ya ce." Gata ñan ki tambayeta amma ni ki daina tuhumatta akan abinda ki ke zargi."
Na dube ta sosai ina fad'in." Kin ce kin san komai a kaina har irin rayuwar dana gudanar kafin na auri d'an uwanki to ina so ki gaya mini mai ki ka sani a kaina mai muni  ki gaya mini kuma ki ba ni sheda da hujja a sannan ne zan saurara miki don na rantse da buwayar Ubangiji wannan lafazin naki ka iya kai mu ga hukuma domin dai ba zan yarda ki yi mini sharri ba."
Ta fara kame-kame murya a dashe take cewa." Ai tsayawa yi miki bayani bata lokaci ne Amina kowa ya san abinda ki ka yi kina budurwa da kuma rayuwar zawarcin da ki ka yi a baya abinda duniya ma ta sani me yasa kike neman sheda da hujja a kaina ."
Wanzar na tashi daga inda nake na nufe ta jikina har kyarma yake yi ta d'an tsorata domin ko ga yanayin yadda ta mayar mini da martani a tsorace take kuma tashin da na yi da azama na nufe ta ya bata tsoro dalili d'azu ta sha mari a kaina ta zage ni yanzu kuma ba ta san abinda zai faru ba.

Na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Yana zaune yana kallonmu bai ce mana komai ba.
Na ce." Ai dole sai kin gaya mini da wane namiji a kama ni a hotel ko kuma lokacin da nake sharafina a social media update dina ya fito wannan hujjar ita kadai nake so na ji daga gare ki"
Ta d'an ja baya tana ta'be bakinta ta furta." Ba ta mini lokaci ki ke yi a banza ke ce ba ki sani ba amma har yanzu akwai sauran hotonanki a wayoyin wasu mazan...... Ba ta kàrasa na fitar da hannu na tsinka mata wani mari wanda ban san ma na iya shi ba.
Ya taso da sauri ganin ta 'baci a lokacin da take han'koran rama marin da na yi mata ya shiga tsakiyarmu yana fadin." Me yasa za ki mare ta Amina zan 'bata miki rai fa."

Ya rike ni da kyau na fizge na bi ta gefensa na janyo rigar jikinta botiran suka zube. Ta yi saurin dafe kirjinta. Ya juya da sauri ya tura ni na zauna d'abas a saman gado zuciyata na harbawa. Ban yi tsammanin zan iya yin cacar baki da kishiya ba sai gashi yau tsananin bacin rai da takaici na nema ya sanya ni na hada jikina da Hauwa da zumar kokawa so nake yi kawai na dake ta sosai mu fitar da raini tunda na gama gane irin sharrin da take so ta la'kaba mini.
Ya rike ta da kyau ya hana ta zuwa wajen da nake zagi kuwa sai auno mini shi take tana fad'in sai ta rama marin da na yi mata wallahi."
Ya furta." Yana da kyau ni ma naga hujjar nan Hauwa sai na gazgata maganarki kada ki ga na goyi da bayanta ki sanar da ni abinda ki ka sani a kanta.
Ta yi shiru tana huci! wannan karon hawaye bai fita ba.
Ya riko hannunta suka zauna gefan gado yana tsakiyarmu yana fad'in." Ba ki fa da gaskiya Hajiya akan wannan maganar ni ma ba zan iya barinki ba domin kina ko'karin mini 'bata mini sunan matata, lallai ya zama dole na ga sheda Amina ta ga sheda ko kuma ki bata ha'kuri a ciki biyu za ki yi daya. Idan na ga shedar abinda ki ka fada a kanta ni ma za gazgata muddin kuwa ki ka gagara kawo sheda dole ki bata ha'kuri ki kuma nemi afuwarta amma ki sani ba zan iya hana ta ta bibiyi hakkinta ba."
D'akin ya d'auki shiru na wani lokaci kafin ya ce." Ya kuke so a yi muku yanzu na kwanta na fad'i na mutu shine burinku ashe da raina zan ga wannan masifar."
Ta ce." Abinda ya fi haka ma za ka ga ni wallahi mutukar ba ka d'auki mataki akan dukan fuskata da ta yi ba idan ba haka ba zan d'auka da kaina duk abinda ya faru a gidan nan ka yi kuka da kan ka."
Ya ce." Babu abinda zai faru sai alheri Hauwa idan kin kashe Amina ko kin yi mata wata illar sai dai na taya ki da addu'a domin kuwa da hannuna zan d'ankawa hukuma ke."
Ta ja hanci ba ta ce komai ba.
Na fara ko'karin tashi domin barin wajen ya rike hannuna tamau ya d'an kalle ni kafin ya sauke ajiyar zuciya ya kamo hannunta yana fad'in." Ku shirya don Allah ba don ni ba kada ku yi gaba ko ku illatar da juna."
Na dube shi da mamaki wai yau shine yake yi wa wani wa'azin kada ya yi gaba. Abar da ta zame masa d'abiaa.
Na zame hannuna daga cikin nata tunda ya hade mana yatsu ne ya rintse da nasa gabad'aya.
Ya furta." Haka zan kawo yarinyar mutane cikinku da girmanku da shekarunku kuna a matsayin iyayenta masu yi mata gyara ta same ku kuna nuna kiyayyar juna.
Wani bala'in haushinsa ya kama ni. Hannuna na cire daga cikin nasu na tashi tsaye ya dago yana kallona bai ce komai ba na kama hanyar fita raina a b'ace. Ita Hauwa shirin take nema domin tunda ta ji ya riketa har yana rarrashinta ta yi lakwas kuma ko lokacin da ya had'a hannunmu waje daya ba ta yi yun'kurin cire nata ba. Ba ni tsammanin zan sake zama da Hauwa a inuwa daya idan lallai sai na cigaba da zaman aure da shi ya zama tilas ya yi

abu daya daga cikin biyun nan ko na koma gidana na kano ko kuma ita ya canza mata gida......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*145*
Wannan shine abinda na yankewa kaina sanadin da ya janyo mana rikici mai tsanani tsakanina da shi domin na rantse masa da Allah ba ni sake zama da Hauwa a gida d'aya kuma wannan dalilin ya sanya shi kai ni 'kara abinda zai biyo bayan haka ba zai yi mana kyau gabad'aya ba.
Bai d'auki ga'barar kaini karar ba da ya yi iya yin sa domin ganin ya tankawari ni na ha'kura ya kasa sai ya kyale ni ya fara neman shiri da Hauwa duk domin na ji haushi da farko ina zaman falon ganin haka ya sanya na daina zama sai da dalili ita kuma mahaukaciyar sai ta d'auka tsoronta nake ji ina gudun ta rama marin da na yi mata. Daga lokacin da ta fahimci akwai 'yar tsama a tsakaninmu ta dage sosai wajan ganin ta kara juyar masa da tunani wanda gabad'aya rashin nutsuwa da ficewar hayyaci ya  ya gigitar masa da rayuwa yana daurewa ne kawai saboda yana so ya nuna mini ba ni kad'ai ba ce matarsa a banza domin duk abinda suke yi shi da ita bai dame ni ba abinda da dai na yanke a cikin raina yana nan ban janye ba akwai wa'adin da d'iba muddin bai yanke shawara ba zan fita na bar gidan.
rashin sakewa da walwala ta ya assasawa yaran da masu aikin damuwa da farko su Baba Tabawa sun d'auka ba ni da lafiya suka dinga shigowa daya bayan d'aya suna duba ni. Amma da suka fahimci akwai damuwa sai duka jikinsu ya yi sanyi mussaman da suka lura da yadda Hauwa ta saki jikinta take yin annashuwa a gidan kamar ba itace mai matsiyacin 'kuncin rai ba.
Baba Tabawa tun da can ma muka dan yi  maganganu na fahimta don haka ta zame kanta ta same ni a d'aki tana ce mini sai na dage da addu'a da neman tsarin jikina domin dai ta gama fahimtar Hauwa ba ta kaunata kuma idan ta samu dama za ta iya aikata komai a kaina.
A tunaninta wannan k'uncin da nake ciki Hauwa ce ta yi mini asiri domin shiga tsakanina da maigidan. To ba a 'kin ta mutum na amsa mata da to kawai ina kara jaddada mata addu'a kullum a cikin yin ta nake.
Ana haka Fadila ta haihu anti Yagana ta kira ni tana gaya mini ta samu 'ya mace na ce mata ina tafe.
A daran ranar duk da ba girkina ba ne na hau saman da na fi sati daya rabon da k'afata ta taka shi sai dai shi ya biyo ni d'akina yawan sa'in da muke yi a tsakaninmu ya sanya ya daina shigowa domin baya jin sukari a duk lokacin da zan mayar masa da martani magana ce mai zafi wadda za ta yi masa ciwo a raina.

Cikin jallabiya na same shi a can wurin da yake zama da Loptop din sa a gabansa. Ita kuma ta ci gayu da k'ananun kaya matsatsen wando iya gwiwa da wata riga mai hannun shimi breast dinta duk ya ta'be ta d'auki wata hular gashi ta sanya sai kace irin tsotstsun arnar nan. kan sa yana kasa yana ta aiki ita kuma tana motsa masa shayin da ta had'a masa.
Na yi sallama cikin gaggawa ya dago kansa ya kallo bakin kofar. Ido ya zura mini yana amsa sallamar ita kuma ta sai ta had'e ranta ta yi kasa da kanta can ciki ta amsa sallamar.
Gabad'aya kafatanin hankalinsa yana kaina har na zauna kujerar da take fuskantarsa a nutse amma babu walwala a fuskata na ce." Barka da dare."
A tak'aice ya amsa da "Barka dai ya kike?"
Ban bashi amsa ba na cigaba da cewa." Fadila ce ta haihu jiya gobe zan je maiduguri in sha Allahu.''
Kai tsaye ya ce. " To shikkenan sai a shirya tafiyar ko?"
Kasa na yi da kaina ban ce komai ba mamaki dai nake yi yadda ya amince nan da nan bai yi jayayya ba can kasan zuciyata na gaya mini hanyar shiri yake nema shine dalili.
Na yun'kura na tashi da niyyar fita daga d'akin ya dubi Hauwa yana fad'in." Ban ji kun gaisa ba kuma kin yi mini alkawari kan cewa za ki gyara kuskuranki haka dai ki ka gaya mini kwana biyu da suka wuce ban ga ni a aikace ba ."
Na yi gaba ban tsaya jin abinda za ta ce ba. Ai wanda ya ce baya sonka da farko daga baya ko ya zo ya ce yana sonka to k'arya yake yi ya fadi hakan ne domin cimma wata manufa tasa Hauwa ba zata ta'ba k'aunata ba dalilin da ya sanya kenan nake so na nisanta kaina da ita. Idan da gaske zuciyarta babu damuwa mai zai sanya daga na shigo ta 'bata rai jikinta ya mutu saboda ganina.
Na shige na yi tafiyata  ina jin sa yana magana ban juyo ba.
Sai da na leka d'akin yaran na same su duk sun kwanta Mairo na ta gyaran wardrobe dinsu aikin kenan ta yi tsifar kai ta wanke da yake Taburni ta iya kitson hannu itace take yi musu idan an kawo wankin kayansu ta goge ta shirya musu ta ba ni tausayi sosai ita kadai a zaune duk sun kwanta dole a rage mata wani aikin mussaman gugar kaya mai wankin idan ya wanke ya goge ta samu hutu ga tashin asuba haka suke ta fama.
Na ja musu kofar na nufi nawa d'akin da sau'kin zuciya domin Ina so na d'an matsa daga wajan da nake zaune ko zuciyata za ta yi sanyi na tsani na bud'e idona na kalleshi ko na ji muryarsa saboda tsabar haushin da yake ba ni a yanzu. Har ni zai yi wa burga to Ina abin yake Hauwa dai macace amma a rashin mata domin dai da gabad'aya ta sullunce babu wata komad'a a tattare da ita idan har yana so ya tsorata ni ko kuma ya sanya mini kunci ya auro wadda ta fi ni komai shine zan daga hankali don yana soyayya da Hauwa a banza nasan duk buge ne.

don Allah kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina b.

Wanka na yi na sanya kayan bacci na yi kwanciyata a gado ina Kiran sunan Allah.
Na ji ya turo kofar d'akin ya shigo.
Na zuba masa ido har ya zo ya zauna a gefan kafafuna yana fad'in." Kin mayar da ni sakarai mara mutunci ko Amina Ina yi miki magana kin yi banza wulakancin nan ya isa haka wai me ki ka taka ne?"
Shiru na yi ban tanka masa ba ya cigaba da cewa." Hauwa duk ta d'auki matakan gyara kuskuranta kamar yadda ni ma na d'auki matakin gyara akan zamantakewar da muke gudanarwa a gidan nan zan yi kokarin kwatanta adalci."
Na ce." To wannan kuma damuwarka ce idan ba ka yi adalci ba duka za ka ci a lahira."
Bai mayar mini da martani ba saboda ya saba jin irin wad'annan maganganun na fitowa daga bakina sai ya d'ora akan maganarsa yana cewa." A wannan lamarin da yake faruwa kece matsala domin kin d'auki wata hanya ta daban wadda na kasa gane inda ki ka dosa na gaya miki ba ni da ra'ayin raba gidana nafiso yarana su tashi tare domin su shaku."
Na tashi zaune ina kallonsa na ce." To sai ka rabu da matsala mana dole ne kana da da yadda za ka yi a kaina tunda na zame muku matsala ka yakice ta ka huta, ba zan zauna da Hauwa a gida daya ba wannan shine abinda zuciyata ta yanke mini.
Ya furta." Ni kuma ba zan raba gidana ba Amina ni dake shege ka fasa."
Na koma na kwanta tare da cewa." Duk yadda kake jin kanka baka fi karfin hukuma ba idan ba za ka raba gida ba to sai ka ba ni da takardata."
Ya furta." Wannan zoben da na sanya miki a yatsa shi yake nuna cewa ni dake mutuwa ce za ta raba auran zobe muke yi."
Na ciro zoben na ajiye masa shi saman cinya ina fad'in.'' Ai ban san manufarka ba kenan ga abinka nan."
Ya d'auka da mugun haushi da takaici a tare da shi ya dinga jujjuya zoben yana kallona har ya so ya d'an ba ni tausayi na d'auke kaina daga kansa.
Ya ce." Na gode." Ya mayar da shi hannunsa kafin ya sake kallona a karon da bashi da adadi ya ce." Gobe ki ka ce za ki je maiduguri ko?"
"Umm!" Na furta can kasan zuciyata.
Ya tashi tsaye yana cewa" Sukairaju zai kai ki a mota za kuma ki ga sa'ko cikin acct d'inki sai da safe."
Ya kama hanyar fita na ce." Da yara zan tafi domin ina so su ga dangina."
Ya juyo da saurin gaske yana cewa." Wannan ne kuma ba ki isa ba babu inda za ki je mini da yara. Ke dai ki je Allah Ya ba da sa'a."
Na tashi zaune ina cewa.'' Mai kake nufi yaran nan na ta'ba nuna maka wani iko a kansu tunda na haife su  baka da hujja domin ba naka ba ne kai kadai dangina zan kai su domin kowa ya gan su."
Ya ce." Ba za su je ba na fad'a ke dai tunda kin zama isashshiya ga hanya nan ki tafi, yaran ma da ba wani damuwa ki ka yi da su ba yanzu za ki ce za ki je da su wani waje su zauna a gidan ubansu kawai."
Raina a b'ace na ce." Maidugurin ne wani waje kada ka manta fa asalina ne."

Ya ce." Wani waje ne mana ko akwai wani nawa a garin duk danginki ne ke ce ta maiduguri 'yan biyu kuma na kano ne garin Dambatta."
Ya fita da sauri tare da jan kofar da k'arfi.
Bacci rabi da rabi na yi da sassafe duk na gama shirye-shiryena kaya set goma na sanya a akwati na ce Khalil ya kira mini Masa'udu ya shigo ya tsaya bakin kofa muka gaisa na ce ya d'auki akwati ya kai mota.
Na koma na sanyo hijabi dina har kasa lokacin yaran sun gama shirin makaranta amma ga dukkanin alamun Khalil ya gaya musu tafiya zan yi tunda shi ya fita da akwatina.
Suka fito Minal ta rushe da kukan gaske sauran sun yi cirko cirko Usai da yatsa a baki tana tsotsa na cire hannun ina fad'in ke ba za ki daina tsotsar hannu ba sai tasa kuka tabbacin a kusa take dama.
Taburni da Baba Tabawa suka fito Mairo ta fito suka tsaitsaya yaran suna ta kuka har da Khalil ina kallonsa ya tsuguna bayan kujera.
Na ji giwata ta yi sanyi ainun dama kamar kiris suke jira domin koda na tsiri zaman d'aki haka suke shigo mini d'aya bayan d'aya idan sun taso daga makaranta.
Shi da Hauwa suka sauko yayin da nake gayawa Baba Tabawa Fadila ce ta haihu zan je  ba wani abu ba ne.
Hauwa fuskarta a sake ganin abinda yake faruwa ko tana zargin yaji na yi oho a gabanta dai jiya na yi masa maganar tafiya maidugurin amma ban san abinda ya assasa mata sakin fuska ba duk dambarwar da uban yake yi da Minal akan ta sake ni ta'ki sai ihu take yi Hauwan ta zo tana jan hannunta da yake yarinyar a zababbiya ce idan tana kuka sai ta gartsa mata cizo a hannu. Aikuwa ba shiri  ta sake ta matsa gefe. Babu halin na ciccibeta na rarrasheta kamar lukutan baya idan tana kuka d'aukarta nake yi yanzu kuma jikina ya yi nauyi cikin da nake d'auke dashi wata shida ni kaina nauyi yake mini bana iya sunkuyon kirki.
Na ja hannuna duka yaran suka biyo ni dakina.
Na zaune gefan gado su uku duk sun tsaya a gabana 'yan biyu da ita Minal din ta uku Khalil ne bai biyo ni ba. Tausayinsu ne ya kama ni ta kar'fi da yaji Hassana da Husaina sun koyi ha'kuri don yadda suke shakkata ba sa shakkar ubansu wasu lukutan idan suna kiriniya da ido na yi musu gargadi suke shiga hayyacinsu shiyasa ba sa yin iya shegankatar da Minal din take yi dalilin uban yana lelenta ba kuma fin sauran ta yi a zuciyarsa ba kawai yana fad'in sunana ne da ita wai  yana yi  mini kara..
Kawai na ji hawaye ya silalo mini duk wannan k'aunar da shakurar da take tsakanina da yarinyar nan dole na bar wa Hauwa 'yarta domin yaran da na haifa kawai zan hada kan kayana mu tattara a waje daya bana tsammanin barinsu a gidan idan Hauwa tana ciki za mu tafi tare da yarana da mai aikina baba Tabawa kenan su Taburni da Mairo idan suna da ra'ayin cigaba da zama da Hauwa su zauna.
Ya shigo dakin sai na yi gaggawar goge kumatuna. Minal na ta fad'in." Mama zan bi ki unguwa, Mama zan biki unguwa."

Ya tsaya a gefe yana fad'in." In banda neman fitina Amina ai sai ki bari su tafi makaranta tukkuna ki fito ki tafi tunda kin san lallai ne za a iya samun wannan matsalar.
Na yi shiru dai ban ce masa komai ba. Ya zo ya ja hannun yarinyar da ta d'ora saman cinyata Yana fad'in." Yi shiru za ku je unguwa ko?"
Ta daga kanta. Ya dubi 'yan biyu da suke tsaye a kusa da ni sai ya girgiza kansa cike da jin haushi ya kamo hannayensu yana cewa." Zan kai ku da kaina ku je karatu ku dawo da daddare da kaina zan fita da ku yawo kuna so ko?"
Suka daga kai babu wani karkashi a tattare da su.
Jim kad'an da fitarsu ya dawo d'akin ina zaune ban motsa ba tsabar yadda jikina ya mutu. Kawai ya mayar da kofa ya rufe ya tsaya yana kallona sai da na gaji tukkuna na dube shi na dan wani lokaci.
Ya yi kwafa yana cewa." Wato da tafiya za ki yi ban isa ki yi mini sallama ba ko?"
Shiru na yi uffan ban ce ba. Ya cigaba da cewa.'' Yaushe za ki dawo kwana nawa ki ka yanke?"
Na ce." Sati biyu."
Ya girgiza kansa yana cewa." A a ban amince ba a yi sati daya dai Hajiya sati biyun da ki ka d'iba a cikinsa nake tsammanin daurin aurena da yarinyar nan Hajara."
Na ce." To ni ina ruwana ni ka aurowa ita da sai lallai ina nan ko iyayenta ni suka bawa."
Ya ce." Kada ki gaya mini maganar banza da wofi Amina kina d'aga mini murya fa ya ina yi miki magana cikin lumana domin mu fahimci juna kina so ki zage ni wallahil-azimin na gaji da wannan rashin mutuncin da ki ke yi mini a gidana."
Can kasa na ce." Sai ka d'auki mataki ai."
Ya yi shiru yana kallona nasan ya ji abinda na ce kawai ya rasa yadda zai yi da ni ne."
Ya ce ki duba jiya da daddare na sa miki miliyan bakwai ki yi guziri ga 'yan'uwa na can garin naku. Biyar kuma sayi kayan kwalliya na danne kirji kamar yadda al'ada ta nuna Hauwa ma na bata."
Na dubi tsabar idonsa ina fad'in." Ba ka isa ka saye ni da kudi ba wallahi bari ka ji da can ba ni kudin dannar kirjin kake yi mata biyu ka auro kafin wannan cikinsu kwabonka baka ta'ba ba ni ba don haka ban ga dalilin da zai sanya wannan karon munafurci zai sanya ka ba ni kudinka ba."
Jikinsa ya yi sanyi ya furta." To shikkenan na ji zan ciko miki 10m sai ya zama sha biyar ba biya ki shikkenan ko?"
Na ce." Ba ka ji mai na ce ba kenan ba ka isa ka saye ni da kudi ba wanda ka tura mini ma yanzu zan dawo maka da abinka Allah Ya rufa mini asiri."
Sai ya yi shiru hankalinsa a tashe na ji yana fad'in." Allahuma ajirni fi musibati Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!
Ya bud'e kofar d'akin ya fita cikin gaggawa.
Ni ma na tashi da sauri na fito na hange shi yana hawa sama falon babu kowa na fice daga gidan.

Sukairaju na tsaye jikin mota da alama fitowata yake jira tunda tun dare maigidan ya sanar masa da tafiyar ya shirya tsaf. A gurguje muka gaisa da masu hidima da gidan ya bude mini motar na shiga na zauna ina addu'a a cikin zuciyata ya shiga mazauninsa shima kafin ya kunna motar daga can maigadi na ko'karin bude gate din gidan....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*146*
Gida a kawo Fadila tunda haihuwar fari ce kuma dai gidan nata ba shi da wani spece inda Allah ya ta'kaita nasa ne ba ya haya ba ce wai hausawa suna fad'in guntun gatarinka ya fi sari ka ba ni. Duk da haka ya yi kokari tunda d'aki uku ne da kicin da bandaki sai dai dak'unan duka ba ma su yalwa ba ne.
Haihuwa da lafiya akwai anya farinciki yarinyar tana zauna da babyna a hannu tana bashi nono na cika da mamaki kwarai da gaske wai yau Fadila ce ri'ke da jinjiri har tana shayar da shi gani ni uwarta gotai-gotai da ni ban gama haihuwa wato idan da Kamaluna ma macace haka za mu jera haihuwa da shi  duk da Fadila ta girme shi sosai amma dai da mace ne a yanzu da ake yi wa yara auran wuri wata'kila da tuni na aurar ni ma
Yusuran Sahura ma tana can da nata tsohon cikin haihuwa ko yau ko gobe wai a haka ma ta yi 'bari na wata hud'u.
A washe da safe Sukairaju ya d'auki hanyar komawa gida bayan ya karya kummalo. Yawan shige da ficen da ake yi a gidan dangin mijin yarinyar da danginmu suna zuwa ganin jarari Hakan bai ba mu damar 'kebewa sai a daran ranar dana kwana biyu a gidan tukkuna muka zauna muna tattauna al'amura masu yawa. Nan na gaya mata irin abubuwan da suke faruwa tsakanina da Hauwa da shawarar da na yanke sannan da auran da yake shirin yi a tsukin kwanakin nan tunda ya ce satin na sama suka yanke za a daura aure.
Ta dinga mamaki tana fad'a kamar ta ari ba ki wai shi bashi da bakin da ba zai ce ya yi wa yarinyar girma ba ai ana barin halas don kunya wannan babbar asara ce da jin kunya idan har ya amince aka daura masa aure da yarinyar da ko shakka ba ta yi ta ji jinkanya da shi.
Abin ya dinga ba ni dariya ganin yadda ta hakikance da gaske tana ta fad'a tana cewa girmansa ya zube a idonta tunda ya shigo da son zuciya dama can yana so idan ba haka ba daidai gwargwado ya yi wa malamin alheri mutumin ya rushe masa gida ya zamanantar dashi tare da sabunta tsangayu irin na zamani aikuwa ya yi abin a yaba masa kuma idan biya zai yi akan hidimar da ya yi masa ya biya shi mai zai sanya kawai a d'auki yarinya a bashi ya kuma sanya hannu ya kar'ba har yana cewa don babu yadda zai yi ne wannan karya ce tsantsa da yaudara.

Da muka wayi gari ma ta tashi da mita shiga fita dari sai ta yi maganar tana cewa kin yi daidai ya kawo yarinyar su zauna da Hauwa a gidan ke ya canza miki wani idan ma ba zai yarda ki zauna a gidanki na kano ba ai yana da iko anan abujan sai ya samar miki da wani. Irin wad'annan masifun ne ya sanya wasu mazan ko basu da wadata suke rabawa matayensu gida to balle shi da yake da suttura da wadata tunda har abinda Hauwa take yi ya'ki ya'ki cinyewa kawai ya rabawa kowa mazauni sai a samu zaman lafiya.
Na ji dad'i sosai ganin yadda wannan karon anti Yagana ta goyu da bayana na saki raina sosai ina jin sasaauci Kuma ban kunna wayata ba yau kwana biyu kenan wanda nasan yana can yana ta lalubena a wayar bai samu ba.
Sai da na yi wanka na karya kullumalo tukkuna na fito falon na sami yarinyar tare da kawayenta na makaranta sun zo ganin jaririya suna ta tsokanarta sai suka ba ni sha'awa muka gaisa ina yi musu dariya cikin raina ina cewa duk yadda za ta kai ga baku labarin nakuda ba za ku fahimta ba sai ta riske ku tukkuna.
Anti Yagana tana ta gyara kaji a kicin nace." In ban da abinki anti Yagana ai sai ki kira ni na taimaka miki."
Ta ce." Ke ma ba lafiyar ce dake ba Amina na gode Allah ni da ya hore mini lafiyar wannan hidimar ta same ni Dada ciwo ya dabaibayeta nasan da ita za ta zo ta zauna mini"
Na ce." K'warai hakane shirin da na yi yanzu zan tafi can babban gidan ne na duba jikinta zan dan zaga dangi mu gaisa."
Ta furta. Hakan yana da kyau."
Kujera na ja na zauna na kama mata aikin Muna gyara kajin a tare na ce." Na lura yaron nan da yake auran Fadila yana da zuciya wallahi gashi nan komai ya yi na al'ada."
Ta gyad'a kanta tana cewa." K'warai Kam tunda ta haihu yake hidima domin da ta fara nakudar ma bai iya kaita asibitin gwamnati ba kudi ya fitar ya kai ta wanda za a bata kulawa wallahi sai da ta haihu ya kira ya gaya mana."
Na furta." Irin wad'annan matasan ya kamata ace an d'auki aure an ba su masu zuciya da dogaro da kansu da kuma ko'karin ri'ke iyali daidai gwargwado."
Daya daga cikin yan matan kawayen nata ta fito tana fad'in.''Mama ana kiran ki wayar ki." Ta mika mata wayar na riga ta kar'ba domin hannunta gaja-gaja yake fa jinin kajin da take gyarawa.
Ina duba fuskar wayar naga sunan Alhaji Tajuden da haka ta yi serving lambarsa
Na daga tare da sanya mata a kunne ina ji yana gaisheta da mutuntawa kamar yadda ya saba itama ta amsa cikin nutsuwa har tana tambayarsa yara ya ce duka suna lafiya sannan ya yi mata barka da arziki kafin ya fara tambayarta ina nake ya yi ta kirana a waya baya samuna.
Ta dube ni kafin ta ce masa gani nan a zaune. Sai na ji yana cewa da ita ta gaya mini na kunna wayata akwai muhimmiyar maganar da za mu yi.
Ta ce masa to in sha Allahu suka yi sallama.
Ta d'an dube ni a sanyaye tana fad'in." Na ji shi a sanyaye yana magana babu nutsuwa Amina kada dai ki ce da biyu ki ka zo nan garin kar ki ce da ni

yaji ki ka yi akan wannan matsalar domin idan bacin haka ai ban ga dalilin da zai sanya ki kashe wayarki ba."
Na ce." E, to ba yaji na yi ba amma dai Ina tsammanin ba ni komawa Abuja kai tsaye daga na bar nan kano zan sauka gidana na sharad'a tunda ya'ki fahimtar abinda nake nufi."
Ta gyad'a kanta tana cewa." Ba ni son hakan ya haifar miki da wata matsalar Amina amma ni kaina a son raina nafiso a raba muku muhalli sai hankalina ya fi kwanciya.
Na furta." Duk mai hankali da tsinkaye abinda zai duba kenan matsawar muna zaune a inuwa guda da Hauwa ba za a taba samun zaman lafiya ba Shima ba zai huta ba tunda ni dai na zame mata ciwon ido anti Yagana wallahi har mamakin yadda Hauwa take zafafawa kanta a kaina ni kuma ba ta raina kwata kwata ban kuma dauketa a matsayin kishiya da zata daga mini hankali ba. Kawai yanzu nutsuwa da kwanciyar hankali nake buk'ata shiyasa na ce ba ni buk'atar zama da ita a gida daya."
Ta furta." Hakane akwai hujja mai karfi a tare dake ni ma ina bayanki amma yanzu tunda ya ce ki kunna wayarki za ku yi magana ki kunna din mu ji mai zai ce."
Na ce." To shikkenan zan kuna."
Sai da muka gama aikin gyara kajin tukkuna ta d'ora a wuta na wanke hannuna da omo sannan na koma d'akin na d'auki wayata na kunna minti goma sha biyar a tsakani ya kira na daga a nutse na yi sallama ya amsa na gaishe shi nan ma ya amsa babu annasuwa. Kafin ya d'ora da fad'in." Yarinyar Minal tun bayan da suka dawo daga makaranta ta samu ba kya gidan kwanta zazza'bi ya rufe ta ya hau ya sauka har takai da sai da aka yi mata karin ruwa Amina ida ta rasu wallahi ba zan yafe miki ba."
Gabana na d'an fad'uwa na ce." Ban gane abinda kake nufi ba."
Ya ce." Kin ji abinda na fad'a Amina ai kin san ba ki da gaskiya shiyasa ki ka kashe wayarki tsayin kwana biyu."
Na ce." Mayya ce ni ma shiyasa na kama kurwar Minal na taho da ita nan maiduguri to don Allah idan ta rasu ka d'aure ni har igiya ta yi rara."
Ya ce." Abinda za ki ce kenan?"
Na ce." To me zan ce maka ka ce yarinya bata da lafiya saboda na taho da kurwata idan ta mutu ba za ka kyale ni ba to ka d'aure ni don Allah shine abinda za ka yi."
Ya kashe wayarsa jin yadda na bud'e masa wuta idan ba rashin mutunci ba kawai ya kira ni yana ko'karin gaya mini magana ni na d'orawa yarinyar ciwo wane irin bala'i ne wannan ne."
Tsabar takaici da damuwa ban iya zuwa dubiyar Dada ba a ranar saboda jikina ya riga ya gama mutuwa da rashin lafiyar yarinyar da kuma abinda ya gaya mini a kan hakan.
Can wajen sha d'aya ya sake kira na na daga ban ce masa komai ba na ji yana fad'in.'" Za ku gaisa ko?'' Da yaran yake na ji muryar Usaina tana kiran Mama na ce." Naam Usai ina Hassana." Ta ce gata nan." Minal fa?"
Ta ce." Ta yi bacci ta fad'a muryarta tana rawa.
Na ce." Ya jikin nata."

"Da sau'ki ta fad'a kamar za ta fashe da kuka. Na ce." To ba ni Hassana itama mu  gaisa ko Ina Khalil?''
Ta ce." Yana 'kasa da Hassana." Na ji maganarta. "Mama ina yini."
Na amsa "Lafiya lau Hassana ina dariyar da babu nisha'di na ce." Ya kuke ina Mairo." Ta ce." Tana can k'asa Minal ba ta da lafiya."
Na ce." Allah Ya ba ta lafiya na kusa dawowa."
Da sauri ta ce." Yaushe?"
Domin na kwantar musu da hankali na ce." Gobe." Ina ji suka fara tsalle da dariya. Ya kar'bi wayar daga hannunta yana fad'in." Me yasa za ki gaya musu haka Amina kwananki nawa da tafiya."

littafin nan na kudi ne yar uwa kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

A tak'aice na ce." Biyu." Ki ka ce za ki yi sati daya ko kin fasa."
"Ban fasa ba." Na fad'a kai tsaye ina ji yana magana da yaran kan cewa su sauka k'asa wajan Mairo. Na daina jin motsinsu. Ya cigaba da cewa kin ga kuwa idan ba ki dawo gobe ba za su d'auke ki makaryaciya domin kuwa yaro baya mance magana kina dai jin tsalle da murnar da suke yi."
"Umm! kawai na ce na yi shiru.
Ya d'an yi gyaran murya kafin na ji shi yana fad'in." Yanzu kin tsane ni Amina ban yi miki komai ba wai menene lefina anan tare dake duka aka dinga wannan d'auki ba dad'in akan kwantar da ni da Maryam ta yi Malamin nan ya tsaya tsayin daka a kaina har sai da ya tabbatar da tabbatuwar lafiyata na cigaba da rayuwa da iyalina. Yanzu don Allah bai cancanci komai ba ban yi tsammanin zan samu wannan turjiyar daga wurinki ba tunda ai da farko ba haka ki ka nuna mini ba."
Na ce." Har yanzu kuma ba ni da damuwa akan hakan ba. Ai kai ka ga zaka ka iya amma dai Ina gaya maka ba zan zauna a gidan da zaka haye kan k'aramar yarinya kamar Hajara ba babu ni a cikin wannan rashin sanin ciwon kai ba kuma zan kara had'a inuwa da Hauwa ba. Ka canza mini mazauni idan ya zama lallai sai ka zauna da ni."
"Shikkenan za ki zauna gidanki na kano tunda hakan ki ke so amma ki sani za ki dinga d'aukar dogon lokaci kafin ki gan ni."
Na ce." Babu damuwa ai." Ba tare da ya sake wata magana ba ya kashe wayarsa.
Da safe da wurwuri na je na duba jikin Dada alhamdulillahi ta warware sai dai jikin girma idan abin ya motsa mata amma yini muka yi muna hira tana gaya mini abin alherin da ya yi musu a lokacin da ya zo dubata wattanin baya.
Bayan sunan Fadila da kwana biyu na fara shirin tafiya tunda mun gama magana dashi kan yanke zamana a kano abinda dai ban yarda da shi ba shine barin yarana a gidansa na abuja da Hauwa dole za mu zauna akan hakan sai ya ba ni yarana wallahi ta ri'ke na ta.
Ya kira ni yana gaya mini na tafi gobe domin shi ma a goben yake so ya shiga garin kanon saboda juma'ar da za ta zo za'a yi d'aurin auran a Bunkure kamar dai yadda ya gaya mini da farko.

To kawai na ce masa. Ban kuma tafi a ranar da ya ce ba sai a washe garin ranar tukkuna Babansu Fadila da kansa Ya d'auke ni a mota zuwa kano.
Gidan Hajja na yada zango anan shi ma ya kwana da sassafe yana karin kummalo ya d'auki hanya.
Hajja ta dinga rarrashina tana tausata ban san me ya gaya mata ba amma yanayin yadda take rarrashina ya nuna mini cewa kamar ya gaya mata wata magana a kaina wadda take nuni da cewar ni ce yanzu ba ni son zaman lafiya tunda Hauwa ai ta mato a kan sonsa kuma dama kulawarsa da tarasa ne a baya ya sanya take yin hauka da tsananin kishi yanzu kam tunda tana samun abinda take so a wajensa yana juyata son ransa ba zai fad'i aibunta ba. Kuma a lokacin da ta fahimci akwai rikici a tsakaninmu ta bud'e wuta da kissa da ko'karin kafa kanta a wajensa.
Ban katse ta ba na yi shiru Ina ta sauraranta tana cewa itama ta fi so na zauna anan din Hauwa da amarya kuma su yi zamansu a can abuja
Sai yamma direbanta magaji ya d'auke ni a mota lokacin shi bai dawo daga bunkure ba duk da ba ranar ne daurin auran ba na lura da yadda yake ta rawar jiki da kai kawo har an yi masa invitation irin na wata da kuma na kati ya d'ora a status dinsa.
A daran na kira Sahura na ce ta zo gobe da wuri dole sai ta taimaka mini mun gyara gidan.
Can misalin sha daya saura na dare ya shigo gidan.
Na gama shirin kwanciya ya shigo dakin ya same ni. Ya zauna gefena da alamar gajiya a tare da shi da kuma yanayi na damuwa da ta riga ta zame masa jiki
yadda bai yi mini magana ba haka ni ma ban yi masa magana ba d'akin ya d'auki shiru na tsayin wani lokaci
Na ji yana fad'in." Amina   ya kamata mu yi gwajin nan na jini ( gyonotp) da yarinyar nan ko?"
Shiru na yi ba tare da na ce masa komai ba. Ya dube ni yana fad'in." Yadda Malam D'aha ya d'aukaki wannan lamarin ba na tsammanin idan an ci karo da wata matsalar wadda ka iya rusa auran ya janye ku'dirinsa sanin halinsa na magana d'aya da kuma 'kin yarda da zamani da hasashen yahudu da nasara........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*147*
Na d'an jima ina kallonsa tare da yin nazari a kan maganarsa na kasa tantance shin shawarata yake nema ko kuma umarni. Sai kawai na yi shiru ba wai don ba ni da amsar da zan bashi ba maganar ce kawai ta sake jefa ni cikin mamaki tunda har yana maganar gwajin jini (gyonotype) ya shirya kwanciya da yarinyar duk da k'arancin shekarunta kuwa.

Na yi shiru tare da juyar da kaina saboda tsabar takaici. Ya sake maimaita mini maganar . Sai na dube shi a sakarce na ce." Kai duk shige da ficen da kake yi ba ka yi gwajin jinin ba."
Ya d'an b'ata ransa yana fad'in.'' Amina ba kya yi mini lafazi cikin dad'in rai ko kina magana da sa'anki ne abubuwan fa da ki ke yi sun take shari'a kuma suna yi yawa."
Na d'an daidaita yanayina ina ce wa." To shikkenan na ji yanzu me kake so na ce?''
Ya sauke ajiyar zuciya tare da matso ni sosai ya kama hannuna ya rike sai kuma ya had'e yatsunmu ya matse gam. A dan tausashe ya furta." Ke ce abokiyar shawarata shiyasa da na fara wannan tunanin na tuntubeki dacewar yin gwajin jini ko ya ki ka ce."
Wani abu ya sake tokare mini wuya."
A tak'aice na ce." Hakan yana da kyau."
Sai ya cigaba da cewa." Ba ni fatan sake auran macce wadda za mu yi ta haifar yara masu lalura Amina wannan cikin da kike d'auke shi yana raina koyaushe da tunanin abinda za ki haifa mini nake mai lafiya ne ko mara lafiya saboda wannan ciwon gaskiya ne akwai shi. Ba ni so a 'daura auran nan jinina dana yarinyar bai jitu ba ta zama k'aramar bazawara domin ba zan iya kar'bar kaddara a karo na biyu ba wannan shine."
Na dai yi shiru ban ce komai ba ba wai don ba ni da abin fad'a ba.
Ya sake matsowa jikina yana magana can kasa." Ya ki ke ganin ya za mu yi,?"
Na dube shi babu yabo babu fallasa na ce."Fisabillahi me kake so na ce akan hakan?"
"Ki ba ni shawarar yadda zan yi." Ya fad'a yana d'ora bakinsa a dokin wuyana.
Na ce.''To shawarata ku je ku yi gwajin jinin ina ga kamar zai fi alheri."
Na ji hucin numfashinsa yana cewa." Idan an samu matsala na yi yaya da malam 'Daha."
"Sai ka yi masa cikakken bayani zai gane!" Na fad'a ina d'an janye jikina jin wani abu ya fara yi mini yawo.
Ya ce." Ba zai yarda ba Amina."
Na ce." To gaskiya kaima kana da lefi me yasa tun farkon fara maganar ba ku yi gwajin ba idan an tabbatar da daidaituwar jini sai a yi godiya ga Allah idan kuma jinin bai inganta daidai yadda ake so ba sai ka datse maganar da wuri ka kawo masa hujjoji da misalai."
Ya furta." Ba ni da nutsuwa fa Amina tun sanda ya ba ni kyautar yarinyar na rasa sukuni gabad'aya domin ni kaina ba ni son auran irin k'ananu haka koda da k'addarar sake wani auran a tare da ni wadda ta fita shekaru zan aura amma wannan tayi yarinyata da yawa."
Na ce." Hakan kuma bai hana ka nemi shawara wajan gwajin jini ba ko duk da ta yi yarinyata ai ka shirya takarta ko ba haka ba ne."
Shiru ya yi bai ba ni amsa ba.
Wai ni zai yi wa kalaman yaudara na janye jikina ya sake rukunkume ni yana tatta'ba wasu sassa na jikina tare da sauke ajiyar zuciya.

Gabad'aya nema yake yi ya daga mini hankali a halin kuma da nake ciki ba ni buk'atarsa ko kad'an jikin dai yana so walwala da annashuwar da zata bari a tari lamarin ne babu.
Babu yadda bai yi da ni ba a daran a kan dole sai ya kwanta da ni na ce a a gajiye nake ba zan iya ba.
Dole ya ha'kura da asuba ya sake nemana da rarrashi da kwantar da kai ya fara ko'karin gaya mini wasu maganganu wanda suka danganci Hauwa na katse shi da sauri  na nuna ba ni so ban san yaushe ya zama munafikin namiji ba ina ruwana Hauwa tana gamsar da shi bata gamsar da shi ba abinda ya dame ni ba ne.
Na ci da kulafuci kamar dambun kuturu ya ma'kale ni na kasa motsi babu yadda na iya haka nan na kyaleshi ya yi abinda yake so kamar zai shid'e saboda gigita lissafinsa gabad'aya ya kwance.
Da kaina na shiga kicin tunda ya sanya an kawo mini komai na bukata. Na soya doya da kwai da tea sannan na dafawa kaina indomee.
Nan d'akina muka yi breakfast din babu yabo babu fallasa amma dai na kasa sakin jikina duk zantukan da yake akan auran nan da zai yi kawai ina jinsa ne da kunne dalili nema yake yi ya rainawa mutane hankali tunda yadda yake nunawa ko jininsa dana yarinyar bai daidaita ba zai iya yin jayayya da malamin ba yadda tun farko ya amince masa to abu ne mai wahala daga baya ya je ya ce masa ga matsala wadda daga baya turawa suka bijiro da ita tunda ai ko a zamanin annabawa ba a san da wani gwajin jini kafin aure ba haka kuma duka iyaye da kakanni suka ta so.
Da haka dai ya yi wanka ya kintsa ya fita yana gaya mini ya yi baki daga kamaru idan ya gama dashi da wuri zanje bunkure a takaice na yi masa addu'ar dawowa lafiya
Sai wajan daya da rabi Sahura ta zo lokacin ne ta taso daga aiki. Sai bayan da muka ci abinci muka yi sallah tukkuna muka fara aikin gyaran gidan wanda kusan zan iya cewa itace karfin aikin ta shasshare mini ko'ina tas aka yi mopping gidan ya dawo hayyacinsa.
Sannan fa muka zauna ina zolayarta ta yi ki'ba tana ta'be baki kuma da gasken ta yi kiba wallahi alamu sun nuna bata da damuwa tana cin gashin kanta. Idan farko akwai damuwar yanzu makomar auran Idiris ta bayyana ya sanya mata nutsuwa da kwanciyar hankali domin dai alkali  ya tilasta shi sakin yarinyar kamar yadda iyayenta suka buk'ata dalili shedu sun shaida babu abinci ingantacce a gidansa sannan kuma alamu na nuna cewa shi din yafi karfinta ta fannin auratayya. Ya kuma yanke masa kudin da zai dinga aikawa yarinyar na goyon ciki har sai ta haihu ta shayar masa da abinda ta haifa kafin ta yaye ya kar'bi d'ansa a bisa adalci.
A wannan matsayar aka tsaya da shi. Tana gaya mini da gumu ta yi gumu ya rasa yadda zai yi ya gaya mata halin da ake ciki.
Na ce." To Sahura tunda dai ya yi nadama sai ki yi hakuri don Allah kada dukan ya yi masa yawa ki kaddara cewa rabon haihuwa ne ya sanya shi rakito auran yarinyar nan."
Ta ce." Ai ban hana shi kwana a gidana ba Amina kwanciya da ni ne na ce ba zai yi ba. Kuma gidan da ki ka ba ni ya balle ni kwado ya sanya matarsa sun

kwashe kaya sati biyu da suka wuce na sanya a zuba mini 'yan haya a ciki. Abincin dai ina ba shi idan na yi ga waje nan ya kwanta ya tashi amma babu mu'amula ta aure.
Na ce." To kin sake bashi lasisin yawon dare kenan?"
Ta'be bakinta ta yi ba tace komai ba. A daidai lokacin kira ya shigo wayata ina dubawa na ga maigidan ne na ajiye ta katse ya sake kira na d'auka tare da daidaita maganata. Na ji yana fad'in." Na fasa zuwa bunkuren nan Amina gani nan dawowa gida."
A tak'aice na ce." To.'' na riga shi kashe wayar na ajiye a gefana ina tsaki
Ta bata rai tana fad'in." Menene haka don Allah."
Na ce." Da aka yi me?"
Ta gyad'a kanta tana cewa." Wallahi tallahi ki ji tsoron Allah akan mutumin nan Amina."
Sosai na zuba mata Ido da mamakin maganarta haka kawai ba ta san irin zaman da nake yi dashi ba tana cewa na ji tsoron Allah akan sa. Ko da yake dama can ita 'yar dakinsa ce bata ta'ba ganin lefinsa. To mai baka kuma ya ninke munanan halaye ya bayyana kyakykyawan ya za a yi ta fahimci aibunsa tunda ba tare take rayuwa da shi ba.
Ta cigaba da cewa." Menene abin tsaki don ya gaya miki cewa zai dawo gidansa ne fa."
Na ce." Hajiya kamata ya yi ki tambaye ni dalilin dawowata nan ba kawai kai tsaye ki fara tuhumata ba ke matsalata dake kenan ba kya taba ganin lefinsa.
A d'an sanyaye ta ce." Menene to?"
Duk abinda yake faruwa na gaya mata tun daga kan matsaltsalun da yake tsakani na da Hauwa da auran da aka bashi a bunkure.
Ta yi sakato da baki tana kallona gabad'aya bakinta ya mutu da kyar ta ce ni haukan da Hauwa take yi bai dame ni ba Amina sai maganar auran nan da ki ka ce zai yi ai na gane yarinyar da ki ke gaya mini ko ba itace ta kawo mini abinci a lokacin da naje ba."
Na ce." E ita ce.''
Ta zura mini ido tana kallo kafin ta ce." Ai ko nono ba ta dashi wannan yarinyar ba ta isa aure ba don bata da 'barage ba na tsammanin ba ta fara jinin haila."
Na ce." To ya kar'bi dai auranta sai ya cigaba da raino amma dai da kamar wuya tunda d'azu yake gaya mini wai za su yi gwajin gyonotype kin ga kuwa da sha'awar  sabon waje a cikin ransa mussaman budurcin k'aramar yarinya irin wannan ba na tunanin zai zura mata tsayin wasu shekaru."
Ta ce." Don Allah ki daina fad'in haka Amina kunya ma nake ji wallahi yanzu shi sai ya iya tu'bewa a gaban wannan tatsitsiyar?"
Na ce." To me ye a ciki Amina wallahi ki daina mamaki da sha'anin maza abu ne mai sau'ki a wajansa."
Ta yi zugum tana dubana kafin ta ce." Lallai mutumin nan ya ba ni haushi wallahi gaskiya abin bai yi mini ba ya kuma shirya cinye muku fuska yarinyar 'yar cikinku ta kalleku a banzance tunda ai duk ranar da ya kwanta da ita to gabad'aya ba ku da bambanci wallahi.

Na yi shiru Ina nazarin maganarta tabbas hakane ranar da ya kwanta da Hajara to itama daga lokacin za ta ji kanta a matsayin matar gida daidai da kowa. Ba ni fargaba akan tarbiyar yarinyar amma yau da gobe idan zama ya yi zama dole wasu daga cikin d'abiunta su canza dalili itama tana ji kanta cewa matar gida ce."
Sahura bakinta ya mutu duk kaud'in nan nata a kansa bakinta murus ya yi tana jin haushin haka ta yi la'asar ta yi mini sallama ta tafi. Ba ta jima da barin gidan ba ya dawo. Ya yi wanka a dakinsa na sama ya canza ya kaya na shan iska ya sauko kasan ya same ni zaune a kujera Ina kallo ya zauna kusa da ni yayin da kamshin turaransa ya game wajan gabad'aya.

Na dube shi kad'an kafin na janye idona ban ce komai ba.
Sai ya riko hannuna yana cewa." Ta karfi da yaji dai kin zama bebiya giwa wai me ya yi zafi ne uhum?''
Ban ce komai ba na zare hannuna. Ya kamo yatsan da ya sanya mini zoben nan ya sumbuta ya ciro shi daga yatsansa ya sake mayar mini yana fad'in."
Ban yi zuciya ba amma ya kamata ki sassauta mini ki yi mini adalci akan duk abubuwan da suke faruwa ke kan ki kin san abinda ki ke yi ba daidai ba ne ko?"
Na ce." Adalci wane iri kake so na yi maka na hana ka kar'bar auran da aka baka ne? A lokacin daka gaya mini addu'a na yi maka kuma dole sai ka yi hakuri a wannan lokacin tunda ni kaina ba jin dad'in jikina nake yi ba."
Ya d'ora hannunsa saman cikina yana fad'in." Na sani amma me yasa ki ka cire duk wani subsidy a kaina kin daina sona ne."
Ban iya kallonsa ba saboda takaici. Ya juyo da fuskata yana cewa." Zan fasa auran nan fa wallahi ba zan iya ba."
Na yi shiru dai ban ce komai ba daidai lokacin ne Hauwa ta kira shi yana d'agawa ta fara kuka tana fad'in." Minal ce ta suma!"
Ya ki'dime sosai hannunsa har yana karkarwa yana tambayarta ya ake ciki yanzu. Yadda take bashi amsa ya sanya na fahimci cewa k'arya take yi wallahi.
Kawai dai za ta fake da ciwon yarinyar ne ta daga masa hankali.
Ya kashe wayar da tsananin tashin hankali yana fad'in." Ki yi wa Allah da annabi ki tashi mu tafi yarinyar nan Minal tana sonki Amina kada hakkinta ya kama ki tunda ta dalilinki komai yana iya faruwa kada mu yi rashinta.
A nutse na ce." Ka je ka kawo mini su nan gabad'aya zan ri'ke su Ina nan akan bakana ba ni sake zama da Hauwa. Idan kuma za ka canza mata gida ni ta bar mini wanda take ciki sai na koma."
Ya ce." Ba ki ji an ce suma take yi ba. Na gaya miki cewa jikinta ya'ki dad'i wallahi tunda ki ka bar gidan nan."
Na ce." Ni da hankalina sarai babu abinda Hauwa za ta k'irkira ya firgita ni. Minal kuwa Ina tsammanin ma uwarta ba ta kaini sonta ba."

wannan littafin dai na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya yi shiru yana kallona na wani lokaci kafin ya haura samansa. Na dubi agogo biyar da rabi jim kad'an ya sauko cikin manyan kaya babbar riga da 'yar ciki.
Cikin zuciyata na ce." Aiki ya same ka in dai Hauwa ce sharrinta yawa gare shi neman kudi ma wataran sai ka yi da gaske za ka yi."
Ya tsaya gabana yana fad'in." Rarrashi da ban ha'kuri babu irin kalar da ban yi miki ba. Ba a yi maccan da zan dinga kwantar mata da kai tana gara ni kamar gare-gare ba. Ki sani Amina kina da magabata kuma hukuncin saki a hannuna yake sai na ga dama zan yi. Wallahi tallahi zan d'auki mummunan mataki akan abinda ki ke yi mini.
Na ce." Sanar da magabatana halin da muke ciki shi zai kara dagula maka lamari domin wallahi ba zaka taba samun kaina ba. Shekara nawa ina ha'kuri dakai tare da bin umarinnka ina so ko ba ba na so. So kake yi na zauna da Hauwa wataran ta d'auki makami ta farauci rayuwata. Ko za ka gaya mini cewa har yanzu ba ka fahimci irin tsananin kiyayyar da take nuna mini ba. Ka kawo mini yarana na ri'ke a hannuna domin ba zan iya barin su a tare da ita ba za ta iya yi musu lahani ta kowace siga.
Idan ba za ka iya rabuwa da ni ba to bar ni anan din ni wata daula ba damuna ta yi ba. Idan za ka shekara ba ka zo in da nake ba babu damuwa na sahale maka."
Ya cire gilashin idonsa ya sanya hankici ya goge ya mayar dashi idon nasa. A d'an rikice ya sake cirewa ya goge kafin ya sake mayar dashi. Na d'auke kaina a raina ina fad'in zautuwa yanzu ka fara yin ta ka wani binjimo babbar riga. Gaskiya na karyawa Hauwa d'ankwali a wannan ga'bar da alama ta d'auki hanyar rama kashin da ya bata. Na yarda Minal bata da lafiya amma haka kawai zuciyata ba ta amince mini da cewa da gaske ne ta suma ba
Na juya ina kallonsa a lokacin da ya kama hanyar fita kenan abujan ya nufa saboda an ce masa yarinya ta suma. Aikuwa dai ga dukkanin alamu mutumin nan so yake yi ya yi mutuwar tsaye.
Kwana uku da tafiyarsa bai kira ni a waya ba ni ma ban kira shi ba ana hudun ne ya zo tare da yarinyar da akwatin kayanta. Ta ma'kalkale ni tana dariya da shafa fuskata duk garin jikin nan nata sai da ya rairaye ta yi d'an wuya. Ko da na gaishe shi sama-sama ya amsa ya bar wajen. Na ri'ke hannunta muka haura saman a tare yana wanka da ya fito ya gan ni a zaune ya sake d'aure fuska ya d'auki basiline ya zauna can nesa da ni yana shafawa a jikinsa. Yarinyar ta fara zagaye d'akin tana neman abin wasa.
Ni abinda yake yi ma dariya yake ba ni abinda ba zai iya ba. Duk tsananin gabar sa ban san me ya sanya yanzu ta daina tasiri a kan kansa ba domin daga ya fara ma yake bari kwana daya biyu zuwa uku ya fara neman hanyar da za a shirya.
Na ce." Ina 'yan biyu na ga Minal ita kadai ai ba haka muka yi da kai ba."
Ya ce." Tunda kin haife ni Amina ai ya zame mini dole na bi umarininki kada na lalace ko?"
Na danne dariyar da nake ji tana yun'kuro mini na ce." Ban haife ka ba amma abinda yake a hakkina nake tambayarka ni 'yan biyu na ce ka kawo mini."

Ya furta." Wannan din da na kawo miki sai ki yi cilli da ita tunda ai ba gidan ubanta ba ne."
Na ce." Mu yi magana wadda take daidai kuma ta fahimta mu kuma cire son zuciya. Ban ce ba zan ri'ke yarinyar nan ba tunda har ka kawo mini ita amma ba ni son tashin hankali daga kowane 'bangare. Idan har da sanin uwarta ka daukota ta amince da hakan babu damuwa a wajena. Amma ya zama dole a kawo mini yarana."
Ya ce." Wannan ne kuma ba ki isa ba. Ba za ki dinga gindaya mini sharadai ba. Hauwa ta da ba ta yanzu ba ce domin duk yadda ki ke tunanin tana 'kin ki na tabbatar da cewa ba zata zalinci yara ba, kuma sanin da ki ka yi mata ta canza sosai ta kuma kar'bi dukkanin kuskuranta."
Na ce." Babu ruwana wannan matsalarka ce kai da ita. Ni dai Hauwa ko za ta had'iyi al'kur'ani don tsoron Allah da gaskiya ba zan yarda da ita ba domin ita din mutuniyar banza ce mara tsoron Allah."
Ya ce." Cin fuska ne ki dinga kiranta da irin wannan kalaman Amina kwanakin baya kin mare ta a fuska duka ta yi hakuri saboda tana jin maganata."
Na ce." Me yasa baka rama mata ba a lokacin ba, ai da ka sani kawai ka d'aukar mata fansa kuma yanzu ma ai bata 'baci ba ga ni zaune kusa dakai ka rama mata kawai......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700.....0542382124. BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*148*
Share ni ya yi ya tafi ya je ya d'auko rigarsa jallabiya mai yankakken hannu ya sanya a jikinsa ya fesa turare sosai sannan ya sauka kasa ya bar ni da yarinyar a d'akin. Na tashi tare da kama hannunta muka sauka baya falon k'asa da alama fita ya yi.
Kai tsaye kicin na nufa na d'ora sanwar dare gefe guda kuma kasan marata na d'an yi mini ciwo kadan da cijewar kafa gobe alhamis asibiti zan yi sammakon zuwa domin duba lafiyata da abinda yake cikina a auna abinda yake cikin domin tabbatar da lafiya yake kwance.
Duk inda na ajiye kafata nan yarinyar take ajiye tata tana yi mini hirar 'yan uwan nata biyu can kasan zuciyata kewarsu ta ishe ni haka kawai yanzu nake tsananin jininsu a cikin raina ba kuma na tsammanin zan iya bar wa Hauwa su wallahi sai dai duk rigimar da za mu yi muyi ta a shirye nake gabad'aya na gama dawowa daga rakiyar Hauwa.
Bayan sallah Isha'i ya shigo muna d'aki ni da Minal na bata wayata tana game ya buk'aci abinci ya kama hanya ya fita da jin haushi domin ya'ki sakin fuskarsa tun da ya dawo.
Na shirya masa abinda na dafa na hau saman da tire din a hannuna cikin jan kafa daya ta ri'ke mini cikin ya yi mini nauyi ainun.
Na same shi yana waya na ajiye tiran kusa da shi na juya zan fita ya dakatar da ni.

Na juyo ina kallonsa fuskata a had'e sai kuma ya ce" Je ki kawai."
Na kada kaina ba tare da nace komai ba na sauka yarinyar tana ta game cikin nishadi cikin zuciyata na ce ikon Allah kenan ban haifi yarinyar nan ba Allah Ya jarabbeta da kaunata haka zalika ni ma ina sonta sosai domin ba ta d'auko kamanin uwarta ba fuskar ta ubanta ce garin jikin ni kuma na washeta tunda uwar da uban duka sirira ne.
Ya kwana can shi kadai na kwana da Minal da safe na yi mata wanka na shirya ni ma na kintsa. Ruwan shayi kawai na iya dafawa na soya 'kawai zalla na had'a mata tea din ta karya.
Ina yin nawa karin kummalon ne ya shigo ya shirya shi ma da alama fita zai yi da wuri a haka har yanzu babu nutsuwa da cikakkiyar walwala a tare dashi tana ganinsa ta fara fad'in." Baba ka ga." Tana nuna masa wayata dake ajiye game din dana kamo mata tana yi ban kashe ba. Tana ta maimaita maganar "Baba ka gani."
Ya karaso ciki sosai ya kar'bi wayar yana dubawa ya d'an saki fuska yana cewa." Na gani Minal mu gaisa ko?''
Ta daga kanta sai ya mika hannu ya kamo nata yana fad'in." Haka ake cewa ina kwana."
Ta sake daga kanta tana fad'in." Baba ina kwana."
Ya amsa yana dariya wadda ban ga ya yi ta ba tunda ya shigo jiya.
Ya d'an tsira mini ido na wani lokaci kafin ya ce." Ba za ki gaishe ni ba?"
Na ajiye kofin shayin da yake hannuna na ce." Ina kwana?"
Ya amsa a tak'aice tare da tankwashe kafa a gabana. Sai na yi kasa da kaina ban sake ce masa komai.
Ya furta." Had'a mini tea din ma nasha.
Ya janyo flat din dake gabana da soyayyan kwai fefe uku manya na d'auki kofi na tsiyaya masa ruwan shayin nasa madara kad'an da milo domin wasu lukutan ma ya fi shan tsura shima amma dai shi yana shan madarar amma kadan ba kamar Baban Saude da gabad'aya madarar ce ma ba ya sha.
Yana kurbar ruwan shayin yana kallona kamar wadda ya samu tibi can na ji yana fad'in." Naga duk kin tasa kin kara girma ina fatan lafiya." Ya fad'a yana duba yatsun hannuna da suma suka d'an yi kumburi duk irin na masu ciki.
Na ce." Lafiya lau in sha Allahu amma dai yanzu shirin da na yi asibiti zan je ina so su yi mini awo sannan kafata na ciwo amma dai hakan ba matsala ba ne in sha Allahu idan ciki ya yi nauyi ya shiga watanni shida zuwa bakwai akan ci karo da irin wad'annan matsaltsalun."
Ya gyad'a kansa yana cigaba da yi mini kallon kurulla kafin ya ajiye kofin hannunsa ya furta." Za mu je na kai ki asibitin da kaina idan ya so zan yi magana da magaji direban Hajja idan kin kammala sai ya zo ya d'auke ki ku je da Minal ku gaisa." A tak'aice na ce to shikkenan.
A mota yake gaya mini daga asibitin bunkure zai nufa domin dai gobe ne za a daura aure bayan an yi sallar Juma'a akwai zai d'auko yarinyar still su dawo asibitin a tare domin akwai likitan da ya yi magana da shi a sirrin ce zai yi mata (genotype) tunda shi dama tuntuni ya san matsayin jininsa.
Na ce." Wane irin a sirrin ce sai kace munafurci me yasa baka so a san za ka yi aure ka bugo kati kana d'ora shi a status dinka menene abin boyewa.

Ya furta." Ni yarinyar ce ba ni so a gani."
Na ce." Kasan abin kunya ne kenan ko?"
Ya yi shiru bai ce komai ba can kuma ya furta." Babu wata kunya fa akan yin koyi da annabin rahama ni dai a yadda nake garau Amina ba na shakkar zamantakewata da mu'amula ta aure da yarinya irin Hajara saboda nasan kaina zan kuma yi mata iyakacin bakin kokarina. Kawai dai har yanzu abin ne bai kwanta mini a rai ba. Maganar buga kati ai ba wani abu ba ne na bugawa bazawara ma balle budurwa."
Na yi shiru ina auna maganarsa. Ni dai lokacin daurin aure na babu wani kati da ya buga tunda abin duka ya zo mana a bazata sai da aka d'aura tukkuna gidajen jaridu suka sani. Yana nufin Hajiya Maryam ne.
Sai na share ban tanka masa ba duk kuwa da cewa na ji zafin maganar da yake akan yarinya ya nuna budurwa ta fi bazawara kenan ita ya kamata ace an bugawa kati.
Duk tsayin rayuwar da muke yi ban ta'ba ganinsa yana tu'ka mota ba sai yau duk da yake ya ce tafiyar sirri ce har da sanya takunkumi da rufe hancinsa da bakinsa da (fecemark)
Haka muka isa asibitin Malam Aminu Kano yana ta yi mini zantukan marasa dadin saurare tunda duka akan auran da zai daura gobe ne ni Ina nake da wata shawara da zan bashi a ce sai da asiki ya zo gaban goshi tukkuna zai yi gwajin jinin ya so wata matsala ta faru idan ba su samu haduwar jini ba fadi yake yi akwai matsala domin dai shi ba zai iya gayawa malam 'Daha ya fasa ba saboda wannan dalili zai bari a d'aura auran amma fa zai bar yarinyar a gidansu kafin ya yankewa kansa hukunci.
Jin haka ya sanya jikina yin sanyi tabbas wannan son rai ne tsagowaronsa babu yadda za a yi na yarda ya lalatawa yarinya kuruciya wane irin wulakanci ne wannan gwara duk yadda za a yi a yau din idan results bai daidaita ba a zauna zama na mussaman da muhukunta domin su fayyacewa Malam D'aha illar hakan.
Yana had'a ni da likitan da zai duba ni ya yi mini sallama a ka yi sa'a cikin asibitin in banda likitan babu wanda ya fahimci shine tunda motar da muke ciki babu tambarinsa kamar sauran motocinsa na zurga-zurga wanda suke tabbatar da zuwansa waje idan an gan su a ajiye.
Scanning ya ba ni naje na yi da result ya fito ya gama dubawa ya dinga washe baki yana fad'in." Hajiya wannan albishirin ni ya kamata na yi wa Yallabai please a yi mini wannan." Na yi murmushi ina fad'in." To shikkenan duk da bai gaya
mini abinda sakamako ya nuna ba a jikina na ji cewa tagwaye zan sake haifa domin yanayin wannan cikin yanayin cikinsu Hassana sai dai wannan din da d'an bambanci kad'an.
Na ji yana fad'in." Yara maza ne biyu yadda sakamako ya nuna dukkaninsu cikin koshin lafiya sun kuma juya yadda ake so nan da sati hud'u sai ki sake zuwa a yi miki awo domin mu sake tabbatar da yanayin kwanciyarsu.
Cikin zuciyata na kira sunan Allah tare da yin godiya a gare shi.
Na ce." In sha Allahu Dr na gade sosai.

Muka fito dare da Minal da takardar result din a hannuna sai sannan na sanyata a jakata can na hangi Magaji zaune a gindin wata bishiya ya taso da sauri ya karaso tare da risinawa yana gaishe ni na amsa da kulawa ya kama hannun Minal muka nufi inda ya ajiye motar a tare.
Hajja ta ji dadin ganinmu su biyu kacal a falo ita da Kamalu suna hira yana 'bare ta mata lemo zaki.
Ta dinga washe bakinta ganina da Minal tana cewa." Ke yaushe aka kawo ki ne k'awata."
Minal ta no'ke kafad'arta ta'ki zuwa wajanta ta tsaya kusa da ni tare da dafa cinyata.
Na gyara zamana a hankali cikin kulawa na gaisheta ta amsa tana ta yi mini maraba.
Na dubi Kamalu lokacin da yake gaishe ni girma ya yi mini a ido kwarai ya sake yin fad'i da 'barage mazantaka dai ta bayyana tunda dama tuntuni muryarsa ta fashe an balaga ga wani gemu zororo a ha'barsa. Cikin zuciyata na ce yaron nan dai ya rantse sai ya zama d'an izala
Gashi makarantar da ya yi ta almajiranci ba ni tsammanin ta 'yan alhalissuna ce. Kawai dai abinda ransa ya fi ra'ayi kenan yaro ya nutsu sosai cike da wata iriyar kammala ta mussaman zahirin kammaninsa da mahaifinsa ta fito 'baro-'baro bambamcinsu kawai shi Yaya Aminu ba shi da gemu kuma bashi da kuzarin yaron amma duk wanda ya ga Kamalu a yanzu zai tabbatar da cewa hoton ubansa ne
Hajja ta fad'i take daga Ina kuke cikin wannan rana ta k'arfe d'aya Amina."
Na ce." Wallahi Hajja daga asibiti nake shine na ce bari na biyo mu gaisa kawarki mata ta gaishe ki."
Ta sanya dariya tana jan hannun yarinyar tana sake no'kewa a jikina. Ta ce." Ina fatan dai lafiya ko Amina sannunki da ibada Ubangiji Allah Ya raba ku lafiya."
Na ce." Amin ya rabbi Hajja lafiya lau wallahi abinda sakamako ya nuna kenan.
Ta dinga fad'in." Alhamdulillahi cike da godiyar da Allah da jin dadi kafin ta shiga kwalawa iyami kira mai aikinta wai ta kawo mana ruwa."
Kamalu ya ce." Hajja ni me nake yi bari na kawo mata da kaina.
Ya ajiye lemon zaki da yake hannunsa ya nufi kicin da sauri lokacin Hajja ta d'auki lemon da ya gama 'barewa tana mikawa yarinyar da fad'in." Zo ki kar'ba to tunda kin 'ki zuwa mu gaisa."

kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ta kuwa tafi za ta kar'bo lemon saboda rashin kunya gabad'aya muka fashe da dariya.
Ta ce." Yusi ai yau tun safe ya fita kasuwa da yake ya ce bashi da karatu yau shine ya yi sammakon fita amma nan da biyar da rabi za ki gan shi ya dawo."
Na ce." Ya zama sarkin kasuwa ai."
Tana dariya ta ce." Haka ake son namiji ya kasance ai."

Kamalu ya ajiye mini ruwa da lemo masu sanyi a gabana. Na dube shi ina fad'in." Baka da hankali wanene zai sha wannan ruwan da wannan sanyin."
Yana murmushi ya ce." Mama ai na ga ana rana ne sosai ruwan sanyi zai fi kashe miki ishi."
Na ce"D'auke ka kawo mini mara sanyi."
Da sauri ya yi yadda na ce din ya kawo mini ya bude ya tsiyaya mini a Kofi.
Na d'auka na sha na bawa Minal Tasha na ajiye kofin saman plate din da ya kawo ruwan..
Hajja ta ce me za a sanya Iyami ta dafa muku Amina ni dai ce mata na yi ta saka mini danwake."
Na ce." Aikuwa a yi dani Hajja har na yi sha'awarsa. Tana dariya ta shiga k'walawa iyami kira ta fito ganina ya sanya ta risinawa tana gaishe ni na amsa mata da kulawa Hajja ta ce da ita ta kara garin danwaken ta saka shi da d'an dama. Ta amsa cike da bin umarni ta koma bakin aikinta.
Kamalu ya shiga dakinsu tsayin minti goma ya fito da wasu littafai a hannunsa gabad'aya muka bi shi da ido Hajja ta ce." Makarantar za ka tafi da wuri haka?"
Ya ce." E, Hajja amma kafin nan zan biya gidan Gwaggo."
Ta ce." Yawwa gwara da ka tuna mini shiga kicin ka ce da iyami ta baka garin danwaken nan leda biyar sai ka tafi mata da shi."
Ya ce." To shikkenan. Ta dube ni tana cewa." Abu ne na marmari duk ranar da ta yi sha'awa sai ta tsumbula.
Na yi shiru ina murmushi gefe guda kuma ina kara kambaba mutunci da halin dattako irin nata ga kyauta ga kirki Hajja mutuniyar kirki ce sosai Gwaggo ta zama 'kawarta kuma aminiyarta. Na tsinkayi maganarta tana fad'in." Ai ya sanar da ku d'aurin auransa gobe ne a Bunkure ko."
Na ce." Eh ya gaya mana Hajja Allah Ya sanya alheri."
Ta amsa da Amin. Kamalu ya fito da ledar garin danwaken a hannunsa yana yi mana sallama tare da ce mini zai zo cikin satin nan in sha Allah.
Ta dube ni cikin nutsuwa kafin ta furta." Amina Malam D'aha mutumin kirki ne kwarai da aniya kuma mutumin maigidana ne tare na san su abokai ne kuma masu rufawa juna asiri ta kowace siga. Lokacin da Tajo yake gaya mini kyautar auren 'diya da Malam 'Daha ya ba shi na yi farinciki domin sanin da na yi cewa gidan karamci ne da ilimi da addini gidan yi wa al'kur'ani hidima tabbas had'a iri da jinin Malam D'aha abin alfahari ne tare da fatan samun zuri'a nagartattu. Sai dai kuma jikina ya yi sanyi sosai lokacin da ya nuna mini hoton yarinyar na ganta 'yar karama nama sheda fuskarta tunda itace ta dinga dawainiyar kawo mana abinci a lokacin da Tajo ya kwanta ciwo a gidan. A mizani na tunanina yarinyar ba tsarar auransa ba ce domin ya yi mata nisa sosai babu hadi gabad'aya babu dacewa.
Amma a mizani na shari'a hakan ba haramun ba ne domin manzon Allah s.a.w shi ma ya yi irin wannan aure ya raini Nana Aisha har ta kai munzali kafin ya fara rayuwar aure da ita.
Malam D'aha Tajo ya yi niyyar bawa d'iyarsa kuma na tabbatar da cewa da zuciya daya ya kulla wannan al'amarin ba don samun abin duniya ba na

sanshi sosai  a can baya abin duniya bai dame shi ba mutum ne mai dattako da sanin ya kamata."
Ta yi shiru tana sauke ajiyar zucciya. Ni kuwa cikin raina ina fad'in anan dai bai san ya kamata ba Hajja tunda har ya iya bawa dattijo yarinya karama irin wannan ai zamanin annabawa daban da wanda muke ciki yanzu.
Ta cigaba da cewa." Na bashi goyon baya akan ya kar'bi kyautar da aka yi masa da kyakykyawar zuciya ku yi hakuri, ku kara akan wanda kuke yi in sha Allahu rabbi ba za ku samu matsala da yarinyar ba. Itama Hauwa zan kira ta a waya domin na kara tausar zuciyata dama itace fitinanniya ku yi hakuri ku kawar da kan ku na dan wani lokaci komai zai wuce."
Na ce." Wallahi babu komai Hajja ai yarinyar bata da matsala zamu zauna lafiya da juna kuma na yi miki alkawari ba za a samu matsala ta wajena ba."
Godiya da sanya albarka har sai da na ji nauyi da kunya na ce ta daina gode mini domin ban yi abinda ya kai ta yi mini irin wannan godiyar ba a ganina ni ce zan yi mata godiya bisa ayyukan alheran da take yi wa a alhalina.
Biyar daidai na fito da niyyar tafiya har lokacin Yusi bai dawo ba fadi take yi zai ji takaici kuwa idan ya dawo ya ji labarin kin zo.
Na ce." Kawai sai ya zo gida ya same ni Hajja ba zan zauna jiran dawowarsa ba zan yi abinci idan na koma."
Muka yi sallama cikin girmama juna da mutuntawa Magaji direbanta ya d'auke ni a mota har gidana.
Sai da na yi magriba tukkuna na shiga kicin jallop nake sha'awa ta taliya da kifi ita na yi na zuba mana ni da Minal muka ci a kwano d'aya na ajiye wa maigidan 'yar kad'an dalili nasan ko zai ci ba dayawa ba tunda ba cimarsa ba ce taliya da makaroni. Abinda ya fi so dangin towo kowane iri sakawara funkaso ko wainar masa ta bauchi Yana son faten doya ma abinci da miya bai dame shi sosai ba sai ya ce asa masa miya kad'an saman shinkafa. Yana kuma son gurasa da miya sosai.
 Wajan goma saura ya shigo tare da Sukairaju ashe tare suka zo garin. Ya d'an tsaya daga bakin kofa ya kar'bi wayoyinsa daga hannuna ya gaishe ni na amsa babu yabo babu fallasa ya juya da sauri ya fita shi kuma ya karaso wajan da nake zaune hannunsa ri'ke dana Minal
A d'an hargitse yake gaskiya tsabar ma baya hayyacinsa gilashinsa a hannu yake abinda bai ta'ba faruwa ba duk rintsi da wahala baya cire gilashin nan na idonsa, sai sau daya lokacin da ya fad'i a garin bunkure yana dawowa hayyacinsa kuwa ya mayar da abinsa kamar wanda aka haifa tare da shi na ta'ba tambayarsa ko yana da matsalar Ido ya ce mini a a yana sanya shine domin kara karfin gani kuma dai ya zame masa jiki idan ma Babu shi a idonsa baya jin dad'i......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA,#700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*149*

Na zura masa ido jikina a sanyaye ga dukkanin alamu akwai matsala. Da kyar na bud'e bakina da ya yi mini nauyi na ce masa barka da zuwa. Ya amsa yana ri'ke hannun Minal da take ta jan babbar rigar jikinsa. Da ya amsa mini bai sake cewa komai ba ya wuce. Na bi shi da kallo cikin lissafi a zuciyata shin menene ya gigita shi hakane? ko dai akwai matsala ta fannin daidaituwar jini shi da yarinyar tunda ya gaya mini zai ce ya d'aukota a yi mata genotype din tunda shi ya sanya nasa As ne kamar yadda nake As. Idan hakan shi ya hadda masa wannan gigicewar lallai ya fito da abinda yake cikin ransa wanda yake ta nuku-nuku da shi yana kuma so ya yaudare mu kan cewa baya son auranta. Alamu sun nuna lallai zuciyarsa ba ta so faruwar hakan ba.
Na tashi na bi shi saman na same shi zaune gefan gado Minal na ta wasa da agogon hannunsa da ya cire ya ajiye shi kuma yana zaune ya dai cire babbar rigar ya ajiye amma har yanzu yana cikin rashin hayyaci.
Motsin shigowata ya sanya shi dubana. Bai janye idonsa ba har na isa kusa da shi na zauna still idona a kansa a takaice na ce." Me yake faruwa ne?"
Ya yi jim kafin dube ni da wani yanayi ya furta "Yarinyar As ce Amina. Akwai matsala tunda ni ma As ne duka d'anjuma ne da d'anjummai, gidan Malam D'aha cike yake da ba'ki na nesa dana kusa sun d'ora manya tukuwane domin abincin jama'ar d'aurin aure dalili shi mutum ne na mutane k'warai da gaske da yawa jamaarsa ta mahaifina ne cikinsu wad'anda suka rage da iyalinsu babu wanda bai san da maganar wannan auran ba. Babban abinda ya fi d'aga mini hankali anan shine yadda zan gaya masa cewa a janye d'aurin auran nan saboda wannan matsalar da bai zama lallai ya yarda da ita ba tunda ke kan ki kin sani abu ne mai wahala ya amince da koyarwar yahuduwa a matsayinsa na malamin addini kuma mutumin karkara."
Na yi shiru ina kallonsa zuciya na gaya mini ba wannan dalilin kad'ai ya sanya shi gigicewa ba akwai wani dalilin dai da yake boyewa.
Na ce." Yanzu wace shawara ka yanke?"
Ya yi shiru kawai yana kallona sai da na sake maimaita maganata tukkuna ya furta." Ban yanke ba har yanzu Amina bana jin zan iya dakatar da Malam 'Daha dangane da abinda ya niyyata ya kuma yi gangami a kansa."
Na furta." Za ka bari a d'aura auran kenan ?"
Ya gyad'a kansa yana kallona."
Sai na ce." To idan hakane menene abin damuwa tunda ka ji ka gani me yasa za ka daga hankalinka. Ka bar wa Allah wata'kila sai ka ga kun samar da yara masu lafiya ba irin wanda ake tsammani ba."
Ya ce." Ai ba wani sonta nake ba Amina. Maccan da nake tsoron rabuwa da ita itace nake jin zan yi hakuri na zauna zaman aure da ita idan aka ci karo da wannan matsalar ga misali nan a kanki. Amma ina ji ina gani ba zan yi gangancin ba gaskiya magana kenan."
Murmushin takaici na yi kafin na ce." Akwai zalinci tsantsa idan har abinda ka fada da gaske ne a cikin zuciyarka to bari na gaya maka daka kai har malamin kun zalinci yarinyar nan. Ya kamata duk wani b'oye -boye da kake yi ka fito fili ka yi wa mahukutanku bayani nufi na walliyanku wai shin kai karamin yaro ne? A tunanina saurayi dan shekara a shirin da biyar ba zai

yarda a yi masa irin wannan kutsen ba ya yi shiru sai dai dama idan yana so. Idan ka bari aka daura maka aure da yarinyar nan to dama kana sonta a cikin ranka. Soyayyar da za ka nuna mata da iyayenta a yanzu ka fito musu da gaskiyar abinda yake zuciyarsa kuma ka gaya musu babban dalilin da ya sanya ka janye nasan ko wasu basu yarda ba wasu daga ciki za su yarda tunda duka yanzu kai ya waye."
Cike da kosawa ya ce." Na gaya miki Amina Malam D'aha fa ba zai ta'ba amincewa da wannan batun ba. Akwai shi da hujja wadda zai fatattaki duk likitan da na kai masa domin ya fahimtar da shi. Ni dai da bakina ba zan iya furta masa cewa na janye ba saboda ga dalilina akwai hujja mai karfi a wajensa.
Na ce." To shikkenan na ji idan an d'aura menene makomar yarinyar abinda nake so na ji kenan."

na kudi ne don girman Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Ya daga kafadarsa yana fad'in." Wallahi ban yanke hukunci ba tukkuna amma dai ina jadadda miki ba ni yin zaman aure da ita. Na bari a d'aura auran domin kada na katse masa hanzari bayan tarin jama'ar da ya gayyato gidansa ana ta hidima. Akwai ciwo da takaici a ce an fasa abin zai yi muni da rashin dad'i."
Na ce." Babban abinda zai yi masa muni shine a daura auran ka bar masa yarinya a gida a jingine wannan shine asalin cin mutunci da wulakanci don haka wallahi kada ka fara."
Ya zura mini ido yana kallona kafin ya sauke ajiyar zuciya a sanyaye ta furta." Ya zan yi to Amina na gaya mini dalilai na."
Na ce." Gobe tunda sai an sakko daga sallar Juma'a za a daura ka buga sammako ka d'auki likitan da ya yi muku genotype din ku je dashi gaban malamin ya yi masa cikakken bayani tare da illolin ciwon da yadda yaran da aka haifa suke shan wahala iyayensu ma suke cikin wuya duk a dalilin ciwon. Ubangiji sai ya dubi zuciyarka ya sanya malamin ya fahimci abinda ake so ya gane."
Ya ce." To idan an yi haka mu yi yaya da jama'ar da muka gayawa wasu daga mutanansa fa na ce miki sun zo gidansa a cike yake da jama'a."
Kai tsaye na ce." An yi haka da yawa ai ba a kanku za a fara ba irin wannan idan kaddara ta gifta sai wani ya maye gurbi. Idan hakan ya kasance yadda muke so kun fahimtar da malamin ya gane sai ka yi gaggawar kira na a wayar zan nemawa wani auranta sai a daura da shi kawai."
Ya yi sakato yana kallona na ce." Wannan itace  hanya mafi sau'ki da za ka warware matsalarka ni ma zan baka gudumuwa daidai  gwargwado amma idan har ka bari aka daura auran da wata niyya a zuciyarka ka cutar da yarinyar sosai kuma ba ka yi wa malam 'Daha adalci ba.
Ya rike hannuna tamau yana sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Na gode giwa Allah Ya yi miki albarka kaina ya d'aure gabad'aya a yanzu neman mafita nake yi."
Ni ma na sauke ajiyar zuciya a nutse na ce." Na kawo maka abinci ko?"

Ya gyad'a kansa yana fadin." Kawo mini."
Na tashi na fita. Lokacin dana dawo yana bandaki na zauna gefan gado Minal tana tsakiyar gadon nasa a zaune tana ta wasa kira ya shigo wayarsa. Minal ta d'auko wayar ta miko mini tana fad'in." Ana kiran wayar Baba, Mama ana kiran wayar Baba."
Na kar'ba na duba sai na ga mamanta ce Hauwa. Na ajiye wayar har ta katse ta sake kira a daidai lokacin da ya fito da toilet din ya zo  da sauri ya d'auki wayar yasa a kunne.
Ya amsa gaisuwar da take yi masa. Jim kad'an ya ce." Malama na ce."A a itama Aminar za ta dawo nan cikinku in sha Allahu."
Ya d'an yi shiru yana sauraranta can kuma ya ce." To shikkenan ku zo ke da yaran gabad'aya ku sauka a gidan Hajja zan yi magana da Ade ku yi duk shirin da za ku yi yau da daddare."
Ya yi shiru yana sauraranta na dan wani lokaci sai ya ja tsaki ya cigaba da cewa." Wai sau nawa zan gaya miki ne gidan ba shi da spece din da za ku zauna ku biyu can gidan Hajja akwai part dina ku sauka a can hakan ya yi ko?"
Ya sake yin shiru dai yana sauraranta ta jima kuwa tana yin magana kafin ya ce." To na ji za a gyara in sha Allahu, zan kira ki da safe kafin ku taho."
Ya kashe wayar yana kallona kafin ya ce." Hauwa ce wai ita dole sai ta dawo kano itama yara kuma can duka suke karatu gobe Juma'a na ce su zo gabad'aya lahadi da sassafe mu koma gabad'aya har dake."
Shiru na yi ban ce masa komai ba. Su zo na ji dadin hakan na kwashi yarana cikin sau'ki komawa kuma sai dai ya koma da ita da yaranta amma ni mun dawo nan gabad'aya a nema musu wata makarantar.
Ganin na yi shiru ban ce masa komai ba sai hankalinsa ya sake kwanciya domin ya d'auka na yarda. Jallop din taliyar da na yi tsammanin ba zai ci da yawa ba wadda na rage masa kaf ya cinyata ya sha ruwan da lemo yana gaya mini tun tea din da muka sha tare a d'akina bai kara cin komai ba.
Abinda ya faru kenan da assuba yana dawowa daga sallah ya fara kimtsawa na yi ko'karin gama abin kari da wuri domin ya karya kafin ya tafi.
Gabad'aya duka a dame yake haka dai ya zauna yana karyawa yana gaya mini jikinsa gabad'aya a mace yake domin baya tsammanin Malam D'aha zai amince da duk wani bayanin da za a yi masa. Na ce." Ka yi ta addu'a Allah Ya zab'a maka abinda ya fi alhari kawai idan har ya amince na gaya maka ka sanar da ni zan nemawa wani auranta ."
Ya amsa mini da to shikkenan.
A gabana ya kira likitan ya yi masa bayani sosai yadda zai tsara malamin duk da aikinsa ne wayar da kan jama'a akan mas'aloli masu yawa a matsayinsa na likita amma dai ya kara tunasar dashi cewa wajan wanda za su je babban malami ne kuma mai tsauri wanda boko bata ratsa shi ba sai tsantsar tauhidi da kadaita Allah ."
Ya kira Hauwa ta ce sun taso tun wajen shida yanzu kuma k'arfe shida da rabi kenan sun yi minti talatin akan hanya.
Har mun yi sallama zai tafi ya dawo yana tambaya wai sai na gaya masa wanda zan nemawa auran idan dashi bai yi yuwa ba.

Na ce." Me kake ci na baka na zuba, za ka san shi in sha Allah."
Sai kawai ya girgiza kansa babu kuzari ya furta." Sai na dawo." Ya fice da sauri Minal tana fad'in." Baba sai ka dawo."
Ya daga mata hannu ba tare da ya amsa ba ya fita.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*150*
Na sake sauke ajiyar zuciyar da ba zan iya lissafa adadinta ba.
Hannun yarinyar na ja muka nufi d'aki ina mamakin sha'anin Hauwa ni yanzu ma ta daina ba ni haushi da mamaki dariya take ba ni wallahi.
Gefan gado na zauna kafafuna na dan rawa haka kawai nake jin faduwar gaba da fargaba akan wannan sha'aninan wani sashe na zuciyata na gaya mini bai zama lallai malamin ya yarda da duk wani nau'in bayani da za a yi masa ba akan wannan lalura. Wanda na gama fahimtar cewa abinda shima ya assasawa  maigidan gigita kenan da damuwa da kuma rashin nutsuwa. A nasa tunanin  idan malamin ya kafe akan ra'ayinsa sai kawai ya bari a d'aura auran wanda hakan ba ita mafita ba tunda da wani kudiri a ransa da kuma abinda ya niyyata akan yarinyar wanda yake nuna tsantsar son zuciya da rashin tausayawa kuruciya. Malam D'aha Malami ne kuma mutumin da ne kuma mutumin karkara wanda ba shi da wayewa da ilimin zamani na boko abu ne mai wahala duk bayanin da za a yi masa akan illar ciwon ya amince da cewa ba kutse aka yi wa shariar Ubangiji ba gashi dai  bincike domin samun mafita ya sanya har manyan likitoci da shugabanni suka kafa dokar yin gwajin jini kafin k'ulla rayuwar auratayya ta din-din don samun sahihan yara masu wadatacciyar lafiya.
Jikina a mace na dauki wayata dake saman dirowar gefan gadona
 babu wanda na yi wa sha'awar auran yarinyar Hajara sai Usaini. Yaro ne nutsatstse mai kuma zuciya tun yana yaro ba shi da matsala har zuwa yanzu da ya kai munzalin girma. To sai dai kuma hanzari ba gudu ba anan shine duk da bai zama dole ba wata'kila Usaini yana iya zama As tunda ni ma itace mun had'a uba uwa kowa da tasa. Na ji daga bakin mutane da dama cewa yana iya canzawa a wasu lukutan amma zuciyata ba ta gazgata hakan ba a ganina idan har sakamako na farko ya nuna matsayin jini da wahala ya sake canzawa. Can kasan zuciya na ji tana gaya mini cewa babu lallai Usaini ya kasance As don kin kasance Amina. Wannan hasashen na zuciyata ya kara sanya mini kwarin gwiwa sosai
 Har indai k'addara ta raba auran da za a daura shi a yau kuma za su ba mu yarinyar zan yi farinciki da hakan domin kuwa duk inda ake neman nutsuwa

da tarbiya yarinyar ta kai daidai gwargwado kuma ta yi sa'a da auransa tunda shi ma bai wuce ashirin da takwas ba.
Bugun farko ya daga na ji shi cikin kasuwa da hayaniya a wajen da yake. Sama-sama nake jin maganarsa na ce." Har ka fita kasuwa Usaini k'arfe nawa yanzu.
Yana dariya ya furta." Takwas saura anti akwai ba'kin da muka yi daga nijar sun yi sayayya jiya mun had'a musu kayan ba su samu damar d'auka ba sai yau da sassafe suka yi mini waya yanzu na shiga kasuwar ma anti."
Na ce." Allah Ya taimaka idan ka sallame su kazo gidana na sharad'a na zo garin yau kusan sati daya kenan akwai maganar da za mu tattauna."
Ya furta." Ba na son rufe shago anti afuwaa zan iya jira Hamusu ya zo tunda sai tara da rabi yake zuwa kasuwar."
Na ce." Babu matsala ka jira shi idan ya zo sai ka taho ina sauraranka."
Sallama muka yi na kashe wayar na ajiye zuciyata na yi mini wani nazari. Kada fa Ummansu ta bijire akan wannan yun'kuri nasan ba ni da matsala da yaron haka zalika ba ni da matsala da Babanmu Ummansu Saminu itace birkitacciya dama tana jin haushi tana ganin duk sabgata idan ta tashi ba a gayyatarta gidana na abuja bata ta'ba zuwa ba Ummansu Hadiza ce ta je sau biyu ta jima tana yi wa anti Yagana wannan korafin tana gaya mata ita ba mu d'auketa a matsayin uwa ba duk hidimarmu idan ta tashi sai mu nemi Ummansu Hadiza kuma abin ba haka ba ne Ummansu Hadiza ta fita shishshigi ita kuma duk abinda zai faru sai ta ce lallai sai an gaya mata ba idan ba mu sanar da ita ba sai ta k'ullaci abin a cikin ranta. Itace damuwata kawai tunda d'anta ita take da iko da abinta idan ta ce bata yarda ba babu yadda zan yi dole na ha'kura amma zahiri na yi wa yaron sha'awar yarinyar.
Na nemi lambar anti Yagana ta katse  ba ta daga ba ina sake kira kuwa ta daga muka gaisa ta ce." Ya ake ciki Amina Ina fatan babu matsala rashin sukuni ya hana ni kiran ki na ji ya ake ciki."
Na ce." Alhamdulillahi babu matsala ina ganin zan ci nasara akan abinda nake so in sha Allahu dama dalilin da ya sanya na kira ki wata shawara nake so mu yi shin ya ki ka ga ni?"
Duka na kwashe abinda yake faruwa na gaya mata. Ta ce." To ai wannan ba matsala ba ce Amina alheri fa ki ke niyyar k'ullawa ban ga dalilin da zai sanya mahaifiyarsa ta nuna rashin amincewarta akan hakan ba ke din Yar uwasa ce kuma ba za ki had'a shi aure da yarinyar da ba ki tabbatar da tarbiyarta ba. Bayan dangantaka ta jini ke uwar dakinsa ce a karkashinki yake idan tana da kunya ai ba zata kalubance ki ba."
Na ce." Hakane anti Yagana amma a cire maganar uwar d'akin nan na dai zauna a matsayina na 'yar uwarsa dalili anan shine ba ni so shi da mahaifiyarsa suga don yana karkashina zan juya masa rayuwa a yanzu ma idan ya zo zan fara tambayarsa shin yana da budurwa tsayayyiya idan ya ce bashi da ita sai na gaya masa shirina. Ina da tabbacin ba zai bijire mini ba."
Ta ce." Misali na yi miki ai idan ta yi tsalle ta nuna d'anta sai a nuna mata ke kuma uwar dakinsa ce a kasuwa sanadinki har yake saya mata atama super ta daura ta yafa mayafi mai tsada ."

Dariya ta kama ni ina fad'in." Anti Yagana kenan, to kin ji dama dalilin da ya sanya nace bari na gaya miki kafin na yanke hukunci Babanmu bashi da matsala hakan zai yi masa dad'i."
Ta ce." Ni ma na baki goyon baya amma kafin nan ki fara tambayarsa genotype dinsa da blood group idan ya sani shikkenan idan kuma bai san matsayin jininsa ba sai ya yi maza yaje a yi masa

Na ce." To shikkenan haka za a yi in sha Allahu anti Yagana a gaishe mini da masu jegon."
Ta ce." Gasu nan suna bacci gabad'aya tunda aka yi wankan safe suka kwanta." Na yi dariya ina fad'in." Fadila manya a shafa mini kan Shahida." Sunan anti Yagana aka sanyawa yarinyar sai uwar tace tana so a dinga kiranta da Shahida a lokacin da ta fad'i hakan na ce wata shekarar sai ki haifo Shahid. Kunya kuwa ta kamata na ce to idan ba rashin kunya ba duk muna zaune ita zata za'bawa 'yarta suna ai ta yi kara ta bari a samu sunan da za a dinga kiran yarinyar tunda ai dole a sakaye dalilin sunan uwarta ne.
Goma da sha biyu ya kira ni a waya ya shigo gate amma maigadi ya hana shi shigowa. Na sanya hijabina na fita harbar gidan suna daga can bakin gate har da Ayuba direba.
Ganin fitowata ya sanya ya kafe babur dinsa Yana kallon Ayuba yake cewa." Idan shi zai ce bai gane ni ba ai kai za ka sheda fuskata ko ba kai ba ne direban da ka dinga zurga-zurgar kai su asibiti a lokacin da Babanmu ya kwana rashin lafiya."
Ayuba ya dinga fad'in." Tabbas ni ne yanzu na sheda fuskarka ka yi hakuri wallahi d'ayan muka fi ganewa." Yana nufin Hamusu. Shi kuma Usaini haushi ya ji yadda suka tsayar dashi a bakin gate suna tuhumarsa domin ba mu yi kama ba ko daya gashi kuma ya ce musu shi kanina ne kuma zuwansa daya gidan shiyasa suke yi masa wanna titsiyar Hamusu suka fi shedawa."
Ayuba ya biyo shi a baya yana dan bashi ha'kuri na ce ya je kawai babu komai suma suna kan aikinsu ne babu lefi don sun ga bak'uwar fuska sun nemi dalili.
Da yake safiya ce ko ruwan da na ajiye masa bai sha ba muka gaisa sosai da bayan rabuwa zafin nemansa ya sanya shima ko gidana na Abuja bai taba zuwa ba kullum yana kasuwa a sanin da na yi masa tun Yana yaro manemi ne baya zama duk wasu lissafe-lissafe da za mu yi ta waya muke yin komai kamar dai yadda muke yi da Hamusu abinda ya gaya mini shima Usaini haka zai gaya mini sun yi bala'in cirar tuta a wajena dalili kuwa anan shine ni kaina sai dai na ce dukiyar itace tawa ta farko kenan da na zuba domin gudanar da kasuwancin abinda zai ru'banya daga baya kuwa duk kokarinsu ne kuma duk inda suka hango cigaba da sauri za su gaya mini a jarraba ko za a samu nasara. Shekara na yi kuwa za a yi lissafi a fitar da riba da uwar kudi a sallami kowa hakkinsa. Usaini yana tura kayanmu gari-gari ta hanyar yanar gizo an san shi sosai kamar dai yanzu da yake gaya mini ba'ki sun zo daga nijar domin sayan kaya ba ni tamtama a online suka had'u."

Ya dinga jan Minal da wasa tana janyewa na rashin sabo har sai da ya samu nutsuwa tukkuna na dube shi a tsanake na ce."kasan dalilin kiran ka da na yi?"
Ya girgiza kansa a hankali yana fad'in. A a  anti amina Allah ya sa lafiya."
Na ce." Lafiya lau kuma alheri ne."
Sai ya saki fuskarsa sosai har da gyara zama yana fad'in." To Ina jinki anti ko za mu sake bude wani shagon ne?"
Na ce." A a matar aure na yi maka."
Saranda ya yi ya zare ido yana fad'in." Matar aure anti a ina take kuma? ban gama gini na ba dalilin da ya sanya kenan na janye idona daga kan 'yan mata domin ba ni so na fara soyayya da budurwa iyayenta su ce na fito. Ni kuma nafiso sai na kammala komai a tsanake sai na nemi mai hankali daidai da ni na aura."
Murmushi na yi Ina kallonsa yana ta jero mini bayani wanda na tabbatar da cewa gaskiya ce tsantsa kuma duk maganar da ya furta tana fitowa ne da can kasan zuciyarsa.
Na ce." Maganar gini mai sau'ki ne Usaini don ma dai ka d'auki irin na zamani da kyale-kyale ai da tuni ka gama ko ba shine wanda ka ta'ba turo mini ta waya ba kwanaki."
Ya ce." Eh shine gidan anti amma yanzu aiki ya kara nisa."
Na ce." To alhamdulillahi Usaini wata yarinya ce na yi maka sha'awarta nutsatstsiya kuma 'yar Malamai idan har Usaini ya samu nasarar mallakar yarinyar nan ina yi masa albishir da cewa ya gama dacewa da ma'aratussaliha."
Ya yi murmushi yana fad'in.'' Kai anti Amina wannan yarinyar a ina take yadda na ji kina kwarzantata wallahi har kin kwadaita mini ita a cikin raina."
Nasa dariya ina cewa." Ka ji d'an gari ko, sai ma ka ganta doguwa chocolate color ga ka farar fata yaranku za su zama wata kala masu kyau."
Ya sunkuyar da kansa yana murmushi."
Na ce." Ka amince kuma ka bar mini wuka da nama a hannuna?"
Ya gyada kansa yana fad'in." Na amince anti Amina wallahi ba ni da ja kuma ba ni da haufi a kan ki na yi farinciki da wannan zabin da ki ka yi mini tun banga yarinyar nan ba har ta zauna a zuciyata.
Fuskata ta kara yalwata da annashuwa na ce." Aikuwa na gode sosai na ji dadin wannan alfarma da ka yi mini amma yau din nan nake so ka sanar da Ummanku duk abinda yake faruwa kuma ina son sanin matsayin jininka."
Ya ce." Zan gaya mata a yau din in sha Allah. Matsayin jinina kuwa( O) ne genotype (AA)"
Wani irin sanyi ya sauka a zuciyata shikkenan an samu yadda ake buk'ata ta wannan bangaran akwai dacewa da cancanta wancan bangaran ne kuma ban san wainar da suke toya ba. Gabana ya fadi na daga kai na dubi agogo sha daya saura kuma yadda suka tsara jadawalin d'aurin auran bayan an yi sallar Juma'a ne.
Na saki ajiyar zuciya ina fad'in ." Ma sha Allah ta kowane bangare an samu daidaito idan har Allah Ya kaddara wannan auran Usaini ina yi maka murna sosai domin ka yi mata."

Ya ce." Na gode sosai anti Allah Ya saka da alheri ya kuma kara girma abinda ki ke yi mana na zumunci Ubangiji Allah sanya miki a mizani Allah Ya jikan iyaye da kakanni."
Na dinga amsawa da Amin Amin Allah Ya taimake mu gabad'aya."
Muka yi sallama kafin kafin ya tashi na gaya masa zuwa dare zan kira shi domin karin bayani.
Ya kama hanya ya tafi na zauna cike da nazari da zullumi hankalina kuma yanzu ya yi can garin bunkure ko a wane hali ake yanzu bai kira ni ba nasan kuma tuntuni ya isa garin tunda babu wata nisa.
Na d'auki wayata gabana na d'an fad'uwa na lalubi lambarwa wayar na shiga sai dai har ta katse bai daga ba. Na sake kira a karo na biyu nan ma bai daga ba jikina ya mutu na ajiye wayar da rashin kuzari."

BUNKURE.
Cike gidan yake zuri'ar Malam D'aha 'ya'ya da jikoki kadai sun isa gayya ba sai sun gayyatowa kowa ba. Amma da yake wannan sha'anin na mussaman ne a gare shi gidan cike yake da nau'in ba'ki daga gari gari nasa da na matayensa mussaman uwar bikin uwargidansa mahaifiyar amarya wato Inno.
An gama towon d'aurin aure suna ta malmale shi a leda ana zuba shi a manyan kuloli gefa guda kuma kirigar tukuwanan miya ne guda biyu kan murhu suke ta cin wuta suna zab'abbaka da tashin kamshi mai shanana a saman miyar.
Yaran mata surukan gidan suna can bakin turgijejiyar bishiyar darbejiya da ba a samu nasarar tun'buketa ba a lokacin da aka sabunta gidan suna ta d'aura zobo a leda suna zuba shi a wani mazubi mai girma. Kowa ka gani cike yake da annashuwa da farinciki daka kan iyayen 'ya'yansu da jikokinsu da surakansu.
Zaure malamin kuwa daga can bayan gidan akwai kofar da aka yi masa ta mussaman domin ba'kinsa wanda Malam Rabi'u ya buk'aci da a yi hakan dalilin gidan akwai matansu babu cancanta maza ma bambamta na shiga gidan kai tsaye duk da sashen malamin daban yake amma dai tilas ta tsakargidan za a bi kafin a isa zauran nasa kuma wasu lukutan iyalansu na fitowa.
Ta wannan kofar suka shiga zauran malamin shi da Dr Iliyas ba kowane ya san da zuwan na su ba.
Malam D'aha na sanye da manya kaya babbar riga da 'yar ciki shadda mai kyau daidai gwargwado da d'inki manya cike yake da Kamala da nutsuwa amma kana duban fuskarsa za ka gane cewa lallai yana cikin farinciki dalilin wanzuwar wani lamari da wata'kila ya jima da shi a zuciyarsa.
Tun bayan gaisuwar da suka yi da shi sai jikinsa ya kara mutuwa kwarai da gaske ya ji a ransa baya buk'atar wannan annashuwar da take fuskar malamin ta dusashe domin kuwa lamarin da suka zo dashi gare shi babba ne wanda zai iya rushe duk wata walwalarsa.
Lallai ne akwai buk'atar zama akan wannan mas'alar mai sark'akkiya kamar yadda mai d'akinsa ta gaya masa ya makara a yanzu ba lallai ne malamin ya

yarda da uzurinsa ba tunda ai ya jima da bashi yarinyar mai yasa bai kawo tasgaro ba sai yanzu da aski ya zo gaban goshi
Jikinsa ya yi tubis bakinsa ya mutu d'akin ya d'auki shiru bayan gama gaishe-gaishe daga shi har Dr Iliyas din sai zare ido suke yi domin dai malamin bai fito ba sai da shirya Kuma yawanci irin wad'annan malaman masifar kwarjini ne da su da cika ido.
Dr Iliyas duk 'kumaji da karsashinsa na k'wararran likita sai da jikinsa ya mace ganin yadda wanda ya gayyato shima jikinsa ya yi la'asar  sai rarraba Ido yake yi yana sinne kai wannan lamari yana da wahalar fahimtarwa a wajen irin wad'annan mutanan da tauhidi ya yi wa k'awanya da kuma rashin samun ilimin boko mai zurfi ga kuma rayuwar karkara abin dai goma da ashirin.....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700....VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWA PEN*
*07084653262*
*151*

Suka yi shiru gabad'aya jikinsu a mace kamar ba wad'anda suka zo d'aurin aure ba mussaman shi angon da gabad'aya rashin nutsuwa ya gama bayyana a tare da shi.  Ana haka Malam Nuhu ya shigo shine babban d'a ga malam D'aha daga shi sai Rabiu amma shi ba a cikin gidan yake zaune ba yanzu da can dai ya zauna dai a gidan kafin daga bisani ya gina nasa a gaba da gidan Malam din da kad'an
 Sa'ida lokaci yakan tafi cira ni Katsina idan an samu amfanin gona ya je ya kasa ya sayar matansa hud'u daya ta rasu sai uku yanzu da yara ashirin da bakwai. D'aurin auran ya kawo shi ya kuma kwana biyu cikin iyalinsa kafin ya koma.
Akwai sanayya a tsakaninsu tun lokacin kuruciya amma dai ba kamar yadda suke da Malam Rabi'u ba domin dai shine sa'ansa. Malam Nuhun ya d'an girme shi tunda sakon Malam Rabi'u ne girman dai ba wani mai yawa bane sai dai da yake shi mutumin karkara ne duk ya manyata sosai ya tsofe ga d'auwaniya da lissafin rayuwa ga hidimar iyali duk mai mace uku a yanzu da yara sama da ashirin da biyar kuma yana ciyar dasu kowace rana babu tangard'a lallai shi ya kamaci da a kira namiji dalili anan shine da yawa maza mace daya ma suna gaza ri'ke ta balle mace biyu da yaranta. Suna nan birjik a gari wad'anda jima'in kawai suka sani duk dare babu fashi sai sun yi amma ba su san hanyar da za su kula da abinda jin dadinsu ya haifar musu ba domin kuwa jin dadin ai shi yake kawo albarkar 'ya'ya bayan an rabauta da shi.
Aka shiga gaishe-gaishe da tambayar bayan rabuwa. Daga lokacin ne ya dan samu nutsuwar bud'e bakinsa da ya yi masa masifar nauyi kasantuwarsu da malamin a d'aki ya kasa duban wajan da yake zaune saboda tsabar jin nauyi da kunya tare da zullumin abinda zai biyo bayan uzurinsa. Ya zurawa Malam Nuhu ido yana nuna Dr Iliyas cikin ko'karin jaddada jarumtarsa ya ce."

Wannan sunanshi Dr Iliyas Musa k'wararran likita ne da ya karanci fannoni da dama yana aiki a babban asibitin nan kano wato Malam Aminu."
Malam D'aha ya sake mikawa Dr Iliyas hannu suka yi musabaha a karo na biyu bayan wadda suka yi da farko a lokacin da suka same shi shi kadai a zauren nasa. Malam Nuhu Shima ya mik'a masa hannu baya suka sake yin musabaha cikin dai karamaci da kulawa.
Wajan ya d'auki shiru na d'an wani lokaci. Kafin ya yi gyaran murya ya cigaba da cewa." Wato Malam Nuhu na ji dadin zuwanka a yanzu saboda wani babban uzuri wanda ya assasa mini rashin nutsuwa da kwanciyar hankali da tunanin yadda zan tunkari Malam da wannan uzurin da duka ya shafe mu gabad'aya."
Shiru ya sake ratsa wajan a karo na biyu babu wanda ya tanka Malam Nuhu dai kacokan ya mayar da hankalinsa gare shi yana sauraransa. Ya nisa kafin ya sake tattago jarumtar da neman rinjaye dangane da abinda yake faruwa ya cigaba da cewa." Wani abu ne da ya zama ruwan dare ko kuma na ce babban kalubale da rikicewar tunani ga ma'aurata wad'anda Allah Ya jarabta da hakan. Kasancewarku mutanan karkara nasan dai da wahala a ce wasu da suke rayuwa a wannan garin ba su gazgata cewa rigafi ya fi magani ba. Kuma hausawa suna cewa taya Allah kiwo ya fi Allah na nan."
Malam Nuhu ya ce." Yallabai ya kamata ka yi magana kai tsaye domin wallahi gabad'aya ka sanya ni cikin nazari da zullumi." Ya dubi malamin yana fad'in." Ko ba haka ba ne Malam?"
Malam D'aha ya gyad'a kansa cikin nutsuwa ya furta."Tun zamansu a wannan wurin na fahimci da akwai abinda yake tafe da su domin dai tunda aka fara hidimar nan Alhaji Tajo bai ta'ba bugo mini sammako irin yau ba sai kwanaki biyu da suka wuce da ya zo da kansa ya d'auki Hajara ya ce da ni za su je asibiti a zaman da nake yi a yanzu ina sauraran ji daga gare shi ne ko Hajara tana d'auke da wani ciwo wanda mu ba mu san da shi ba sai yanzu."
Malam Nuhu ya ce." Ya Malam Hajara kalau take domin tunda aka haifeta a gidan nan bata ta'ba kwanciya wani mummunan ciwon da zai gigita mu ba. Kusan a yanzu ma duk ta fi yaran gidan kuzari da hankali."
Ya gyada kansa amma bai ce komai ba. Suka dai zuba masa cikin yanayi na damuwa gabad'ayansu domin ga yanayin yadda ya fara yi musu magana sun san lallai akwai matsalar da take shirin faruwa.
Ya sauke ajiyar zuciya kafin ya cire shakku da jin nauyin malamin ya dubu idonsa sosai ya ce ." Malam a gafarce ni idan har na yi lefi ina neman afuwa. Ban zo nan na d'auki Hajara na kaita asibiti domin a yi mata wani gwaji na mummunan ciwo ba face samun nutsuwa da ita domin ingantuwar auranmu da kuma samun yara masu albarka da wadatar lafiya."

Na kudi ne littafin nan kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya gyada kansa yana fad'in." Babu cutuwa ko cin zarafi tsakanina da zuri'ar Alhaji Ibrahimu kai din daidai kake da wannan da yake zaune a gefanka." Ya

nuna Malam Nuhu. A daidai lokacin Malam Rabi'u ya shigo da daurikan goro kusan bakwai ya jibge a gefe d'aya.
Yazo ya zauna a ka gaisa da shi yanayin da ya gan su a cikin na alhini da zullumi ya sanya ya fara tambayar d'an uwansa lafiya.
Malam Nuhu ya furta." Lafiya ba lafiya amma dai mu saurare daga Alhaji Tajuden."
Duka suka zuba masa ido sai ya cigaba da cewa." Ina godiya Allah Ya gafarta Malam wannan da yake zaune da na gabatar muku da shi shine likitan da ya yi mana gwajin jini da yarinyar nan Hajara cikin kwarewa da irin hikimar da Allah ya huwace musu ya tabbatar mini da cewa akwai matsala domin kuwa jini na dana yarinyar nan bai yi daidai da yadda ake buk'ata ba. A irin hasashen da suke yi da kuma yadda muke gani a kan wasu da Allah Ya jarraba da samun yara masu d'auke da wannan cutar mai kisa farar d'aya ya sanya shi din ya ba mu shawara a matsayinsa na jami'in lafiya dakatar da abinda ake shirin yi a yanzu dalili anan kuwa shine za mu kasance ni da yarinyar nan cikin yanayi na damuwa da tashin hankali a duk lokacin da Ubangiji Allah Ya ba mu rabo na haihuwa yaranmu za su zo d'auke da wannan lalura ta sikila wadda take kisa a take ta kuma wahalar tare da jirkita hallita da matsancin ciwo mabambamta idan kwana bai k'are ba."
Shiru kamar an yi ruwa an d'auke babu wanda ya ce uffan amma gabad'aya jikinsu ya yi sanyi ban da malamin da wani murmushi ne ma na mussaman a saman le'bansa.
Dr Iliyas ya yi kundubala ya dubi malamin da wasu takardu guda biyu a hannunsa yana bud'a su ya ce." Ya Malam a matsayin mu na likitoci muna yin iyakacin bakin kokarinmu akan kowace irin ma'asala domin mu dora jama'a akan hanyar da za su samu mafita da kuma wadatar lafiya. Babu nufin yi wa Allah shishsigi domin shi Ubangiji shine ya d'an sammana sani daga cikin abinda mu ba mu sani ba sanin abinda yake kudira sai shi buwayi gagara misali."
Malam D'aha ya zuba masa idoo yana sauraransa. Ya cigaba da cewa."Yawaitar wannan ciwo da yadda masu d'auke dashi ke shiga gagari da k'unci na rayuwa da azaba mai tsanani a duk lokacin da ya motsa ya sanya kungiyar manyan likitoci daga 'kasashe daban-daban mahukunta da kuma gwamanti had'a karfi da k'arfe domin yin bincike akan dakile hanyar da wannan lalurar za ta cigaba da yaiwata a kowane sassa na fad'in duniyar nan gabad'aya.
Binciken da k'wararru suka yi tare da taimakon Allah Ya sanya suka gane cewa mataki na farko da za a d'auka domin dakushe yad'uwa da haihuwar yara masu d'auke da wannan lalura yin gwaji na jini domin sanin matsayin namiji da mace a duk lokacin da za a k'ulla auratayya wanda muke kiransa da (genotype) Ta wannan hanyar ne kawai za mu duba mu ga cancanta da dacewa wad'anda suke so kulla aure domin yin rayuwata ta din-din tare da samar da yara masu ingantaciyar lafiya.
Daga lokacin da muka fahimci cewa As da As na da mutukar had'ari a matakin jini ko Ss da Ss Muna yin iyakacin bakin kokarinmu wajan ganin mun hana su kulla aura ba don komai ba sai don gujewa 'kin juna da tsanar

junansu da za su yi a nan gaba dalili kuwa anan shine suna fara haihuwa za su ci karo da jinyya mai tsanani daga albarkar da suka samu. Iyaye na kasance tamkar majinyyata marasa nutsuwa da fargaba a duk lokacin suka dubi abinda suka haifa a kwance cikin mawuyancin hali na ciwon ga'bobi da kumburi da 'konewar jini zafin jiki da koke-koke Mu likitoci muna yin misali da ciwon nakud'a irin na mata ga yaro ko yarinyar da suka  tsinci kansu a cikin wannan yanayin. Nakud'a idan Allah Ya sau'kakawa mace cikin dan k'aramin lokaci zata haife abinda yake cikinta sa'banin mai d'auke da wannan ciwon a duk lokacin da ya motsa masa yana ficewa ne daga hayyaci tare da jefe zukatan iyaye rayuwar ce ko mutuwa.
Ya nisa cikin sauke ajiyar zuciya ya cigaba da cewa." Ita wannan cutar ana gadonta daga iyaye biyu wato uwa da uba kamar yadda na yi muku misali da farko idan ya kasance an samu rashin daidaituwar jini uba ya kasance As uwa ma ta kasance As to akwai yiwuwar su samar da yara masu dauke da cutar kuma mafiakasari yaran da za su haifa duka za su rinjayi masu lafiyar yawa. Akwai misalin Ss da Ss shima kamar As din ne akwai buk'atar ha'kuri da juna tare da neman mafita daga kowane bangare domin gujewa samar da abinda zai zama damuwa da zubar hawaye a gaba.
Kamar yadda Yallabai ya yi bayani da farko kafin ba ni damar magana ni likita ne massanin fannika da dama da suke da ala'ka kowace lalura kuma ina yin iyakacin bakin kokarina wajan ganin na bayar da shawara akan abubuwan da su kawo rud'ani da cutar da wani bangare.
Shin yaya ake gane cewa an haifi yaro da wannan cutar dalili anan shine yaro yana karami ba shi da bakin da zai fad'i cewa ga wajan da yake masa ciwo sai dai kuka da kumburin jiki kafafu da cikinsa da kuma jirkitar launin idanu daga fari zuwa ruwan dorawa (yellow) alamu na farko kenan sai yanayin suffa da rashin kuzari ta wani gefan tafiyarsu ma tana bambamta da irin ta masu cikakkiyar lafiya.
Abu na farko da za a yi shine idan yaro ya nuna irin wad'annan abinda na lissafa da farko ayi maza a kai shi asibiti domin auna shi don tabbatar da lafiya mu kuma a matsayinmu na likitoci daga lokacin muke fara namu taimakon da shawarwari ga iyaye akan yadda za su kula da yaronsu don kiyaye tashin ciwon a kai kai."
Ya yi shiru yana sauke ajiyar zuciya kafin ya nisa cikin nutsuwa." Ya cigaba da cewa." Allah Ya gafarta Malam ban zo nan wajan domin katse sunnar manzon rahama ba face bada shawara a matsayina likita amma ina ji Malamai da yawa na fad'in cewa akwai maganinta mu dai a likitance wannan matakin muka d'auka domin dakushe k'ara yawaitar haihuwar masu dauke da wannan  lalura."
D'akin ya d'auki shiru na wani lokaci kafin ya yi gyaran murya a nutse ya furta." Babu wata cuta da Allah bai yi maganinta ba Iliyasu ban katse maka hanzari ba kuma ban raina sanin da Allah ya yi muku ba a matsayinku na masu taimakawa. Kafin na bawa Alhaji Tajo auran yarinyar Hajara na nemi zabin Allah na kuma yi istahara akan lambarin a kuma duk sanda zan wayi gari nakan tsinci kaina cikin farinciki don ganin zuriata da ta abokina za ta had'u waje daya domin haifar da wata zuriar da ba za mu iya iyakance

adadinta ba. Mu bar wa Allah da ni daku gabad'aya mu yi imani da tauhidi cewa babu mai kashewa da rayawa face shi wannan karamin dalilin da kuka zo gabana da shi ba zai zama silar da za a warware wannan alkawarin ba da ya zama saura k'ankanin lokaci a d'aura shi.
Ba mu isa mu hana Allah abinda ya shirya ba domin duka a can baya tun kafin mu kan mu mu zo duniya iyayenmu suke auran juna ba tare da wannan binciken na nunawa Allah iyakarsa ba. Iyaye suka haife mu lafiya lau babu ciwo ko kad'an mu ma muka rayu lafiya muka auri matayenmu babu ciwo kuma suka haifar mana da zuria masu tarin yawa da ba su d'auke da wata lalura makamaciyar wannan don haka wannan magana da kuka zo mini da ita ba za ta dakatar da ni daga abinda na niyyata ba a yau idan har Alhaji Tajo ba kai zaka nuna mini cewa ba ni da alfarma a wajenka ba."
"Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! abinda yake ta fad'i kenan a cikin ransa zuciyarsa na wani irin dokawa da tashin hankali da damuwa. Babu fa wani dalili da zai sanya shi yin rayuwar aure mai nisan zango da yarinyar nan dalili kuwa shine yana da burin kara samun haihuwa. Tabbas Allah ne mai yin yadda ya so idan ya so zai iya bashi lafiyayyun yara da yarinyar ba kamar yadda yake hasashe ba amma rashin nutsuwa da lamarin ya sanya masa fargaba yarinyar ba tsararsa ba ce gabad'aya  koda an daura masa aure da ita ba ya tunanin zai iya had'a shimfida da ita balle har ta kai ga ta d'auki ciki suka shiga cikin zullumi akan abinda za a haifa mai lafiya ne ko mara lafiya. Amina ta riga ta zama k'addararsa shine dalilin da ya sanya yake ji a zuciyarsa wannan dalilin ba zai sanya ya rabu da ita ba kuma zai iya cigaba da zaman aure da ita. Amma dai a yanzu ba ya tunanin zai sake yarda ya auri wadda jininsa da nata bai daidaita ba.
Maganar Malam Nuhu ta katse tunanin da yake yi ya ji shi yana cewa..........✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*152*
Suka juya gabad'aya suna kallonsa a lokacin da ya fara magana kamar haka.
" Ya kamata a k'ara duba wannan uzurin da suka zo da shi Allah Ya gafarta Malam nasan da wahala Alhaji Tajo ya d'auki aniyyar tozartaka a irin wannan ranar da gabad'aya ta zame mana abar alfahari da farinciki mussaman da muka tabbatar da cewa wanzuwar lamarin shine abinda ka fi buk'ata a yanzu domin sake kulla zumunci mai karfi tsakaninka da abokinka Alhaji Ibrahimu Allah Ya yi masa rahama da gafara."
Suka amsa da "Amin gabad'ayansu kafin ya sake nutsuwa sosai ya cigaba da cewa zahiri wannan lalura da suke magana akanta akwaita kuma har yanzu tana k'ara yaduwa a wasu wuraran da ba su d'auki abinda ya zo a zamanance da muhimmanci ba. Malam ko dai ka manta shekarun baya ashirin da biyu da suka wuce muka dinga dawaniya da mai sunan Inno har

Allah Ya d'auki ranta a asibitin Murtala na cikin garin kano wanda sai a lokacin ne gabad'aya muka san ga cutar da ta zama ajalinta."

ABINDA YA FARU.

Shekaru ashirin da bakwai can baya Malam Nuhu ya auri matarsa ta fari Lantana wadda a yanzu ba ta raye ta rasu dalilin farfadiya tunda tana da mutanan b'oye sa'i da lokaci sukan tashi. Auran soyayya suka yi a cikin kauyen nasu kamar yadda al'ada take duk da wannan lalurar tata ta farfadiya hakan ya zauna da ita tunda yana sonta shi kansa mahaifinsa ya bashi gudumuwa kwarai wajan yi mata magani idan ciwon ya tashi. Da ta samu ciki sai wahalar da take sha ta sake ru'banya tunda kowa ya san yadda masu wannan ciwon suke shan ba'kar wahala a duk lokacin da iskar ta buge su a kan titi ne ko a kasuwa ko a gida sun dinga katantanwa kenan da jikinsu suna malkwadewa tare da taune lebensu da kumfa dafara mai hade da jini.
Suka dinga bige ta a kai akai don babu wanda ya tsammaci za ta haife wannan ciki da yake jikinta lafiya saboda yadda take jigata.
Cikin ikon Allah da lokacin ya zo ta haihu kalau aka samu 'ya mace wadda ta ci sunan Inno Ramatu suke kiranta da Rahma. Tun tana yarinya jinjira ta fara nuna alamun rashin lafiya ido ya jirkice daga fari zuwa yellow cikinta ya yi kurcici sai siraran kafafu da hannu. Da masifar kukan tsiya da zafin jiki domin koyaushe idan aka ta'ba jikinta radau ake jikinsa. Da yake kauyene a wancan lokacin da babu wayewa sosai kamar wadda suke ciki a yanzu sai duka daga can b'angaran iyayenta dana shi Malam Nuhu suka alak'anta lalurar da yarinyar take yi akan shafar aljanu dalili uwarta tana da su kuma sun tashi sosai a lokacin da take d'auke da cikinta a jikinta..
Suka dukufa wajen yi mata jike-jike na maganin gargajiya daga can b'angaran malamin kuwa yana yi mata rubutu da tofi ana bata tun tana jaririya ta saba da shan sassaken magani mai d'auke da ruwan rubutun da kakanta yake yi mata. Har hayaki sukeyi wa yarinyar saboda duhun kai har rukiya sai da Malam D'aha ya yi mata da abin ya ci tura duk a tunaninsu aljanu ne suke tsotse ta kuma suke hana ta bacci da daddare suke firgitata tana kwanan kuka. Duk wannan wuyar da yarinyar take ci Allah bai amshi abarsa ba sai da ta yi shekaru hud'u tukkuna cikin halin rai da rayuwa domin a duk lokacin da ciwon nata ya tashi hayaki ake yi mata aka dingi bata sassake da saiwa wadda aka dafa da jar kanwa.
Wajan cirani can Katsina uban suke hira da abokinsa yana gaya masa halin da yake ciki da yarinyarsa wannan mutumin a irin bayanin da ya yi masa ya gane cewa babu maganar iska sai dai idan wata lalurar ce shine ya ba shi shawara kan cewa ya kaita asibitin cikin gari na kano general ne na kowa da kowa domin yawanci ma mutanan kauyen sun fi morarsa har ya ta'ba bashi labari shima daga nan k'atsina garinsu ya ta'ba kai mahaifiyarsa asibitin na Murtala aka dubata har ta kwanta na tsayin sati hud'u kuma ta samu kulawa kwarai ya ce masa su jarraba yin na asibiti ko za a dace.
Koda ya dawo gida ya sanar da Malam D'aha da kyar ya amince da a d'auki yarinyar a tafi da ita a ganinsa abinda yake damunta bai had'a hanya da asibiti ba domin duka sun d'auka cewa lalurar uwarta ce ta shafe ta.

Ba a tafi da uwar ba tunda tana halin ciwo Inno kakarta ita ta goyata suka tafi dawowar da yarinyar ba ta yi ba kenan domin kwanansu daya a asibitin ciwon ya tashi da masifar k'arfi likitoci suka dinga kai kawo a kanta inaaa babu jini ya kone ta rasu.
A wannan lokacin ne likitan da yake tsaye a kan yarinyar ya zauna ya dinga yi musu bayanin musabbabin abinda ya yi ajalinta babu iska sai tsananin ciwon da Allah ne kadai yasan maganinsa.
Duka ba su gazgata hakan ba a lokacin suka dawo gida da gawar  yarinyar daga lokacin ne Malamin ya ce kada a sake daukar wani daga cikin zuria'arsa a kai asibiti duk cuta akwai maganinta cikin al'kur'ani mai girma.
Shekara biyu bayan rasuwar yarinyar uwar ma Allah Ya d'auki rayuwarta sakamakon wata fad'uwa da ta yi iskokai da suke tare da ita suka bugeta a bakin kofar bandaki daga lokacin jikin nata ya'ki dad'i har dai rai ya yi halinsa.
Wannan shine abinda ya shud'e a shakarun baya kuma a iya gwagwarmayar da yake da sauraran redio hurd'a da mutane bambamta tunda a can katsina wajan da yake gudanar da sana'arsa birni ne ba kauye ba ya tabbatar da cewa duk bayanin da ake yi akan wannan lalura gaskiya ne ya gazgata itace silar yarinyarsa ta fari Rahma wanda ada can suke d'auka shafar aljanune.

Malaman D'aha ya yi shiru jikinsa ya d'an shika kadan a lokacin da yaron nasa ya tariyo masa abinda ya shud'e a cikin wasu shekaru da suka gabata. To amma shi a ganinsa wannan kadai ba zai hana k'ulla aure ba domin a zamanin baya wanene ya san da yin wani gwajin kafin a yi auran kuma cutar ba ta yawaita ba."
Malam Rabi'u da jikinsa ya gama mutuwa saboda wannan lamari ya furta." Ya Malam a duba wannan lamari a kawo sasanci a cikinsa domin kada a zo a yi abu anan gaba a koka tun yanzu ya kamata a ce an magance matsalar nan domin ana yin aure ne domin samun zuri'a wadatattu kuma masu lafiya muna neman alfarma a duba a kuma yi adalci ta kowane bangare."
A dan sanyaye ya furta." Rabi'u ba na 'ki ba ne zuwa yanzu ni ma jikina ya yi sanyi tunda zamani aka ce, Annabi Muhammadu S.a.w shi kansa ya yi magana akan zamani duk yadda muka kai ga ta'kawa da gudun sa'bawa Ubangiji idan abu na zamani babu yadda muka iya amma abin lura anan shine mu yi yaya da jama'ar da muka tara domin taya mu murna wannan shine abinda ya fi damuna a yanzu."
Malam Nuhu ya furta." Abu ne mai sau'ki Ya Malam kana da almajira da suka 'yantu da yawa wasu sun shiga cikin gari neman arziki kamar yadda ka saba duba nagarta da cancanta a cikinsu ka bashi auran Hajara a daura da duk wanda ka zab'a mata in sha Allahu ba za a samu wata matsala ba daga kowane bangare."

na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Daga can b'angaransa kuwa ya kira sunan Ubangiji babu adadi ya yi tahamidi tare da jaddada godiyarsa a gare shi ganin yadda aka samu kan malamin cikin k'ankanin lokaci ya magantu cikin kwarin gwiwa ya furta." Idan babu matsala an kuma ba ni wu'ka da nama ina nemawa wani aminttaccen yarona auran yarinyar zan kuma zame musu Uba gabad'aya."
Malam Nuhu ya washe bakinsa Yana fad'in." Ka ji wani iko Allah ko Malam ina ganin duk wanda zai fito daga wajen Alhaji Tajo za a samu nagarta da sasihancin abinda ake buk'ata an samu mafita cikin sau'ki sai a juya d'aurin auran zuwa gare shi.""
Malam D'aha ya dube shi cike da damuwa ya furta." Na so tabbatuwar auran nan da raina ya kwadaitu da shi Alhaji Tajuden amma ga yadda Allah Ya juya lamarin muna fatan hakan ya zama alheri da samun abinda ake buk'ata na kuma baka wu'ka da nama akan Hajara."
Ya dinga godiya kuwa kamar wanda ya yi masa gagarimar kyauta Malam Nuhu fadi yake yi mu ne za mu yi godiya fa Alhaji Tajo mune muke da godiya a wurinka.
Ya tashi ya fita tare da fad'in su jira shi lokacin rana ta yi sosai sha biyu da rabi ana ta haramar tafiya massalaci kai tsaye mota ya nufa Sukairaju ya hango shi ya fito da sauri ya bude masa ya shiga ya mayar da kofar ya rufe ya tsaya daga waje tare da harde hannunsa a k'irji.
Ya sauke ajiyar zuciyar da ba zata lissafu ba godiyar Allah kuwa a cikinta yake yi sai dai yana d'an zullumin saurin yanke hukuncin da ya yi bai kira ta ya ji ya ake ciki ba. Shin wane yaro ne take nemawa aure a yadda yanzu malamin ya karrama shi tare da bashi amana baya tsammanin zai yarda da kowane irin za'bi. Idan wanda take nemawa auran bai yi masa ba zai aurawa Sukairaju yarinyar duk tsiya ya fi shi kuruciya kuma ya tabbatar da cewa zai rike masa ita da amana amma hanzari ba gudu ba shine menene matakin jini tunda dai shi a kan haka ya bijire yana da kyau daga kowane bangare ya samu gamsashen bayani kafin a k'ulla auran.
Jikinsa ya sanyi sosai ya lalubi wayarsa dake cikin aljihu sai a lokacin ma ya lura da kiran da ta yi masa.
Ina zaune jikina duk ya yi la'asar ganin d'aya saura na rana zuciyata na tabbatar mini da cewa wannan auran fa sai an daura shi da mijinki Amina tunda ki ka ga har yanzu bai kira ki ya gaya miki wata matsala ba. Dama fa yana so yaudara ce kawai yake yi miki akwai wani namijin da zai ce baya sha'awar budurci mussaman na yar k'aramar yarinyar irin wannan wadda yanzu take tashi.
Na kwanta a hankali saman gado ina kallon Minal tana yi mini 'buruntu saman madubi yaran dake cikina sai wutsil-wutsil suke yi tabbacin suna buk'atar abinci ba ni kuma da niyyar shiga kicin din babu ma kuzari da karsashin da zan iya gudanar da wani abu.
Na tashi da sauri jin kiran waya na d'auka da sauri shine na sanya a kunnena har muryata na rawa na amsa sallamarsa kafin na ji shi a dake yana fad'in." Wane yaro ne ki ka ce za ki nemawa auran yarinyar nan.''
Jin wannan maganar daga bakinsa na ji sanyi ya cikin zuciyata na daidaita maganata ganin yadda yake furta tasa da isa na ce." 'Kanina ne Usaini dazu

na kira shi na gaya masa kuma mu yi maganar genotype domin shine akan gaba kafin komai. (AA) genotype blood group (o)" Duka na zayyano masa wannan bayanin babu hadiyar yawu.
Ya furta.'' Ya kuke da shi Usainin kuma menene sana'arsa kin tabbatar dai da nagartarsa ko domin yanzu amanar yarinyar tana hannuna. Na ji maganar daidaituwar jini amma ina so kada ki rufe mini da son lallai aure ya tashi daga kaina ya koma kan waninki, ki gaya mini halinsa dalili mas'ala irin ta aure mussaman irin wannan da ta zo a jirkice ba a rufi ana fayyace gaskiya daga kowane bangare da ni da ke gabad'aya mun sheda nagarta da tarbiyar yarinyar nan shi wanda ki ke nemawa auran nata nake so na ji bayani na gaskiya a kansa kada ki rufe mini komai a kansa."
Na ji kaina ya wani sara saboda tsananin mamakin maganganun da yake furta mini. Wato da irin abinda zai saka mini kenan. Kwanaki uku da suka wuce ya zama kamar wani mahaukaci saboda tarin damuwa da tashin hankali. Na shiga cikin matsalarsa na bashi shawara domin samun mafita shine yanzu zai juya maganar ta wata siga daban neman mafitata ne ya sanya na ce zan nemawa dan'uwana auranta saboda shi kada ya aureta tunda Ina kishi akan yarinyar. Wannan shine karatun kawai domin duk yadda ya yi maganar a kudindine na fahimta tunda ni ba mahaukaciya ba ce.
Na daure sosai tare da danne tashin hankalin da yake yun'kuro mini na ce." Usaini kanina ne ubanmu daya ba zaka san shi ba gaskiya tunda shi namiji ne kwarai don samun kamarsa a cikin maza a yanzu dai sai an tona yaro ne mai zuciya kuma ba makwad'aici ba. Koyaushe cikin neman na kansa yake yi.  Yana da shagon sayar da zannuwa a kasuwar kwari.
Sannan ya tsayar da sallah ya yi karatu daidai gwargwado na addini dana boko baya sata kuma baya shaye-shaye, wannan shine abinda na sani a kansa. Amma idan kana shakku za ka iya kiran waya idan kana da ido ko wanda kake mu'amula da shi cikin unguwarmu ta kabuga ka ce a yi maka binkice akan Usaini Salisu maihula na lungun itacce sunan layinmu ya yi suna haka zalika ma gidanmu ya yi suna babu wanda bai sani ba tun daga bakin titi zuwa cikin lungun Babanmu fitacce ne."
Ya yi jim daga daya bangaran ina sauraran amsarsa gabana na fad'uwa saboda tashin hankali mutumin nan mara mutunci ne tsantsa kuma mai mance alheri da ni yake magana."
Na ji yana fad'in." Ni da Sukairaju na yi wa sha'awarta shima ai kin sheda nagarta da cancantarsa ko na jima dashi Amina bai ta'ba cin amanata ba."
A takaice na ce." Da shi da Usainin duk daya ne ni a wajena idan ka yarda da cancantarsa a yi dashi kawai Allah Ya tabbatar da alheri."
Ya sauke ajiyar zuciya yana fad'in." A a ayi dai da Usanin kawai tunda yanzu shine sakamakonsa ya bayyana kuma kin tabbatar mini da cewa babu matsala na aminta a yi da shi din.''
Na ce.'' Idan an biya sadakin zan biya ka idan ka dawo a basu dubu dari biyu. Duk abinda ya kamata na al'ada wanda suke yi za mu yi musu."
Ya yi shiru bai ce mini komai ba nasan haushin maganata ya ji. Na sake ce wa." Ka na jina ko idan kuma dari biyu ta yi kad'an daga dari uku zuwa abinda ya yi sama ka biya zan baka kudinka idan ka dawo."

Sai ya kashe wayar bai ce komai ba. Na ja tsaki tare da ajiye tawa wayar zuciyata na tsalle tsabar takaici da b'akinciki da ya guma mini. Wai mutumin da ya rasa mafita ya gigice tare da zama sullutu shine ya yanzu saboda ya samu kansa yake ko'karin juya alheri zuwa sharri. Duk yadda nake 'kin auran a cikin raina ban ta'ba fitowa fili na nuna masa ba saboda gudun irin haka da yake ya iya sharri da lauya zance yana fad'in saboda kada ya aureta na ce ina nemawa d'an uwana auranta. K'warai wannan magana ta tsaya mini  a cikin raina ko da na shiga kicin domin d'ora abinci ina tunaninta da mamakin fitowarta daga bakinsa........✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*153*
Haka na kammala aikin da takaici da kuma farincikin nasarar da Usaini ya samu wajan samun damar mallakar Hajara a matsayin matarsa uwar yaransa anan gaba. Akwai daidaito ta kowane bangare a tsakaninsu babu cuta babu kuma cutarwa yadda yake a nutse haka itama yarinyar take a nutse kuma babu rawar kai da iyayi na 'yan matan yanzu matsalar kawai babu zurfin boko a tare da ita wannan
kuma bai kai ace an damu dalilin rashin samuwarsa ba tunda da akwai na addinin zai kori duk wata tangard'a da za a samu a zamantakewar auran nasu wadda ba mu fatan hakan in sha Allahu rabbi.
Wajan uku saura na kintsa jikina sosai kwalliya na yi irin wadda na jima ban yi irinta ba na zuba lece brown a jikina wanda ya ji stones ta ko'ina ga kyau ga kudi na yi amfani da set din gold dina da ban jima da saye ba.
Tare muka ci abinci da yarinyar kamar koyaushe tana yi mini hirar 'yan uwanta da alama ta yi kewarsu nasan duk yadda aka yi sun iso yanzu suna gidan Hajja.
Ina idar da sallar la'asar ya kira ni dama dakon kiran nasa nake yi domin na ji a ina a akwana.
Ya ce mini an d'aura amma Malam D'aha ya ce angon ya je yana nemansa.
Yadda yake magana kamar wanda aka yi wa dole ni ma na amsa da kalar sigar da yayi mini
 Ya nisa kafin ya sake magana." Ga ni nan a kan hanyar dawowa gida."
A takaice na ce." Sai ka dawo."
Na riga shi kashe wayar ban jira ya sake wata maganar ba.
Kai tsaye Babanmu na kira dama da safe na sanar da shi halin da ake ciki ya ce tunda mijina ne zai kar'bi auran to a bashi dama zuwansu ba shi da amfani dalili ga yadda lamarin ya kasance amma bayan d'aurin auran za su je wajan malamin domin godiya.
Na sanar da shi an daura sannan na tabbatar masa da cewa zan shigo gidan gobe domin mu tattauna da mahaifiyarsa akan yadda za a shirya hidimar biki."

Ya yi ta yi mini godiya da sanya mini albarka Ina kara jin k'warin gwiwa a cikin zuciyata tare da addu'ar Allah Ya taimake ni na cigaba da tallafar 'yan uwana.
Muna gama waya na kira angon na gaya masa cewa an daura ya kuma zo da daddare ina son ganinsa domin mu yi magana akan abinda ya rage na aikin gidansa da yake ginawa.
Mun jima muna waya da anti Yagana tana fad'in idan mun tsayar da magana na kira ta na sanar da ita halin da ake ciki.
Na sauke ajiyar zuciya tare da kashe wayar bayan mun gama da ita. Kiran sa ya sake shigowa a karo na biyu na daga amma ban ce komai ba. Na ji yana fad'in." Kashe mini waya ki ka yi saboda me?" Na yi shiru kawai sai ya cigaba da cewa."
abubuwan da ki ke yi mini sun ishe ni wallahil-azimin zan d'auki mataki mai tsanani a kanki Amina."
Shiru na yi ban iya ce maaa komai ba ganin yana neman fitina a irin wannan lokacin da ya kamata a ce ya kasance cikin walwala a yadda yake nuna 'kunci da damuwa a baya amma kacokan yana neman ya huce takaici a kaina shin wai ko dai yana son yarinyar nan dole ta sanya shi ha'kura saboda rashin daidaituwar jini wannan abubuwan da yake yi sun fara sanya mini zargi da shakku a kansa tunda ai zuciyarsa a kirjinsa take ba a bayyane take ba balle mu ga abinda yake 'boyewa kamar kishi yake yi.
Ya karaci maganarsa ban ce komai ba haka ya ha'kura domin duk yadda ya kai ga so na gaya masa da wanda nake waya har na katse tasa ban gaya masa ba na kyale shi dai ya shigo gidan sai mu yi wacce za mu yi ai waya ta yi kad'an.
Har bayan isha'i bai shigo ba na fi zargin yana gidan Hajja dalili Hauwa da yaran kuma tare za su kwana tunda nan ta zo ta same shi. Usaini ya zo kamar yadda na umarce shi yaro sai annashuwa yake yi ya nuna mini kara da hallaci kwarai ya kar'bi abinda bai ta'ba ganinsa da ido ba cikin girma da mutunci wannan dalilin ya sanya mini sake d'aukar al'amarin da muhimmanci kwarai da aniya. Ya nuna mini gidan nasa a waya ya yi nisa sosai don an yi rufi an sanya k'ofofi a wasu d'akunan da yake filin babban ne part biyu ya yi yana gaya mini d'aya bangaran zai sanya Babarsu ne idan ya gyara mata sai na ce masa mu fara gyara na amarya tukkuna duk abinda ya kamata na ado da k'awata a gida a yi lissafi da ma'aikata daga nan zuwa ranar wata juma'ar a yi kokarin kammalawa domin ba ni son yarinyar ta yi dogon zama a gidansu.
Muka yanke magana a kan haka.
Hamusu na kira a lokacin na ce ya had'a masa lefe akwati shida a sanya manyan kaya daga kan atamfofi zuwa leces abinda ba mu da shi a shago a sayo a had'a a kawo mini na gani.
Ya ce mini za a yi kokarin hadawa kamar yadda na buk'ata.
Muna tare da Minal a falo wajan tara da minti goma na dare ina dokon shigowarsa yaran sune a kan gaba kafin su shigo shi da ita.
Minal ta buga tsalle a guje ta nufi bakin kofa suka rukunkume juna Hassana da Husaina suna cikin wasu 'yan kanti sabbi masu kyau sosai da wani

karamin hijab a wuyansa daga inda nake zaune nake k'are musu kallo na ga sun sake yi mini tsayi ko dai don na kwana biyu ban gan su ba ne oho sun dai yi mini kyau k'warai Khalil na cikin shadda riga da wando da aiki a gaban rigar har da hula a kansa. Ita kuma tana cikin abaya baka mai jajayen dutsuna ta yafe mayafinta a wuyanta har da gilas baki a idonta da jar jaka da takalmi.
Na juyar da kaina cikin nutsuwa na amsa sallamar da ta yi suka 'karaso falon ita da yaran gabad'aya shi kuma ya haura sama ba tare da ya ce komai ba.
Ta zauna kan kujerar da take fuskantata fuskarta a sake kamar ba itace Hauwa mai k'uncin rai ba. Ta zare gilashin idonta tana duba na sosai ta ce."Amina ina yini mun same ku lafiya."
Na amsa a tak'aice ina nazartarta.
Sukairaju ya shigo ya tsaya daga bakin kofa akwati biyu ya ajiye madaidaita don basu da girma kayansu ne a ciki daga nan ya juya ya fita da sauri.
Hankalina ya d'auke wajan amsa gaisuwar da yaran suke jero mini Usai ta zo ta dafa cinyata tana ta kallona sai kuma ta dora kanta a saman cinyata. Na dora hannuna a kanta ina le'ken fuskarta. Hassana cikin narai-narai da ido ta ce."Mama ki ka ce za ki dawo gobe."
Ta fadi maganar muryarta tana rawa kamar za ta yi kuka lokacin na tuna da alkawarin bogi da na yi musu a lokacin ma tun ina maiduguri.
Na ri'ke hannunta amma ban ce mata komai na kira Khalil da hannu Ina fad'in ."Zo mu sake gaisawa."
Ya kuwa taho da sauri yana dariya yake fad'in. Mama mun yi kewarki fa sosai kullum muna labarinki shiyasa da muka zo muka ce mu dai nan a wajenki za mu kwana."
Na ce." Ni ma na yi kewar yarana sosai Khalil ina su Mairo baba Tabawa da Sultan."
Ya ce." Duk suna nan lafiya sun ce a gaisheku Sultan ba shi da lafiya yana zazzabin hak'ori Baba ya ce a bar shi a gida kada a zo da shi."
Na gyada kaina ina dubanta lokacin da take yin magana cikin yar dariya ." Aikam yara sun yi kewarki a gida Amina shi kansa ma gidan kewarki yake yi."
Murmushi na yi ina duban Minal da wayata a hannunta tana latsawa ko kusa da uwar ba ta je ba gefe guda kuma ina nazarin abinda yake so ya faru domin ga dukkanin alamu ba yaran ne kadai suka zo mini kwana ba har da ita tunda ga akwatin kayansu nan."
Na danne tare da furta." Kun ci abiñci a gidan Hajja ko kuwa na kawo muku."

littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Ita ta ba ni amsa duk da ba ita na tambaya ba na ji tana cewa." A alhmdullhi ai sai da muka ci abinci muka fito mun gode sosai."
Na yi shiru ban tanka mata ba ina ta saurararan labarin Mairo a bakin yaran da sa'kon gaisuwar da suka ce a gaya mini.
Wajan goma daidai na tashi na hau saman domin tunda ya hau bai sauko ba ga yara suna so su kwanta. Yadda tsarin gidan yake dama can babban falo

ne da dakuna manya biyu a cikinsa toilet da kicin wanda yake d'auke da store wadatattu.
Saman kuwa dama can d'akuna biyu ne amma daya ne a gyare wanda yake mu'amula a cikinsa tun farkon tarewarta a gidan zaman mace daya ne babu takurawa yanzu kuma Khalil ya zama d'an saurayi ya d'an fara girma babu buk'atar a had'a shi da mata a d'aki daya tunda tun can abujan aka raba musu d'aki.
Yana zaune da jallabiya a jikinsa ya yi wanka yana waya shigowata bata hana shi cigaba da wayarsa ba amma kafatanin hankalinsa yana kaina har na zauna daga dan nesa da shi waya yake yi da Alhaji Sulaiman yana yi masa bayanin yadda al'amarin ya juya har aka d'aura auran da waninsa ya yi masa fatan alheri a yayin da yake ta amsawa da Amin Amin can kuma sai ya yi shiru yana saurarānsa na ji yana fad'in." Anya kuwa Alhaji ba dai yanzu ba tukkuna wad'annan ma fama nake da su amma za mu cigaba da neman zabin Allah."
Daga haka suka yi sallama ya juyo yana kallona 'kuri! Na sake tamke fuskata tare da tariyo maganganun da ya gaya mini dazu amma bari mu ajiye wannan mas'alar a gefe kafin nan ina so na ji dalilin da ya sa ya kawo mini matarsa cikin gidana bayan da bakinsa na ji yana gaya mata babu waje a ina zai sauke ta. Ba ni buk'atar Hauwa gabad'aya a rayuwata bana tsammanin zan iya sake sakin jikina da ita domin bata daga cikin mutanan da Ubangiji ya ce idan sun tuba ku yafe musu Hauwa bana jin za ta yi taubatun nusu'a akan zamantakewa ta tsakani da Allah."

Ya dube ni yana fad'in." Hajja ta ce ta zo cikinmu gabad'aya tunda yaran sun dage anan wajanki za su kwana can kuma ita kadai za ta kasance, amma ni ma na fi buk'atar su zauna a can gidan Hajja saboda ba ni son fitina fa na gaji idan ba so kuke na mutu ba."
Na ce." Ai ita kanta Hajjan ta san gidan ya yi mana kad'an ni wallahi tallahi na gaji da wannan rashin adalci da son zuciya ba ni son had'a numfashina da matar nan domin zahirin k'iyayya ta nuna mini na bar mata can gidan na zo nan na zauna domin zuciyata ta samu nutsuwa ta sake biyo ni ko sai ta yi wa rayuwata illah tukkuna za a gane abinda nake nufi."
Ya 'bata ransa ainun yana duba tsabar idona ya ce." Rashin kunyar ta tashi daga kaina Amina ta yi tsalle ta tafi kan mahaifiyata kenan ko, gidan ki ko nawa da za ki yi mini iko da abinda nake da iko da shi, ki gaya mini gidanki ne ko nawa na ce?"
Ya fad'a cikin 'karaji har yana dukan hannun kujerar da yake zaune.
Duk da na tsorata daga ganin yadda ya burkice na dake sosai ban sarayar da mutuncina ba na ce." Gidanka ne ai dama ban ce gidana ba ne amma dai ni ce yanzu a cikinsa kuma na ce ba ni buk'atar zama da wata a cikinsa. Idan lallai sai ka zauna dani a irin hukuncin da na yankewa kaina na rayu ni kadai da yarana a waje daya babu wata bagidajiya da za ta d'aga mini hankali ko ta nemi halakar da rayuwata. Kuma kada ka sake ka yi mini k'azafi akan maganar da na fad'a domin ni ban ga ta inda na kausasa harshe akan mahaifiyarka ba."

Ya sake hasalowa yana fad'in." A ciki nake dake domin kin jima kina yi mini rashin kunya kala-kala saboda kin samu dama akaina ko kin lura ina sonki da yawa za ki samu damar taka ni yadda ranki yake so kin zo geji muddin ki ka ce za ki sanyo mahaifiyata cikin wannan rashin mutuncin naki wallahi ranki idan ya yi dubu sai ya 'baci."
Na sake aro jarumuta da jajurcewa domin dai duk wannan hargitsin da yake yi bai karya mini lagona ba ko na tsorata na furta ." Kada fa ka yi mini sharri akan abinda ban yi ba babu cin mutunci balle rashin kunyar da kake magana a tsakanina da Hajja wannan alkawari ne na daukarwa kaina."
Ya ce." Idan ba rashin kunya da rashin arziki ba mai yasa za ta bata da umarni ki ce ba daidai ba ne har kina fad'in ita kanta wannan ai wulakanci ne da nuna mutum bai isa ba."
Na girgiza kaina cikin ko'karin nuna masa ba haka nake nufi ba na ce." Idan wannan maganar dana furta akan Hajja ta hasala maka zuciya Allah Ya baka ha'kuri amma zan fita yanzu tunda da sauran dare a gidanmu zan kwana nan gidan Hauwa ne da yaranta kamar yadda wancen ma ya zama nata.
Na yun'kura na tashi a hankali yaran dake cikina suna naushin marata duk da ciwon da nake ji na yi azamar kama hanyar fita.
Ya cimma ni dalili da kyar nake iya cire 'kafa.
Ya tari gabana da b'acin rai a fuskarsa ya furta." Ba za ki bari mu huta ba ko Amina, ba ki duba nauyin da ki ka yi, kin ki ki bari mu fahimci juna har mu raini yaran dake cikinki kin dusashe mini farinciki da annashuwata kina nema ki dasa mini b'akinciki me na yi miki ne?"
Na daga kaina na dube shi a hankali na ce." Ka bar ni na huta ni ma?"
Ya yi shiru bai ce komai ba da akwai alamar sasaauci a fuskarsa. Ya rike hannuna daya na fizge tare da ratse shi zan wuce ya san janyo ni da sauri tare da sanya ni a jikinsa. Na sake cirewa rik'on karfi ya yi wa hannuna. Yana jana ina turjewa so yake mu je mu zauna a gefan gado.
Na ce." Ai babu buk'atar wani zama na samun maslaha da daidaito a tsakaninmu tunda har yanzu baka fi karfin gidanka ba. Zaman sulhu da samun mafita ba za a yi shi da ni ba a yanzu zaman 'yanci zan yi da kare kaina."
Ya ce." Na gaya miki tuntuni Hauwa ta gyara ta daina duk wasu abubuwa na rashin kyautawa kada ki manta da irin yadda na fifitaki a kanta na nuna miki kulawa da k'auna a kanta ki ka fitar da hannu ki ka tsinka mata mari a gabana. Na hana ta d'auka mataki ta kuma hanu. Wannan bai isheki ba Amina."
Na ce." Ai baka burge ni ba daka sani ka bari ta rama marinta ko kai ka rama mata tunda ka ji mata haushi. Ka daure mata gindi tunda baka musanta abinda ta fad'a ba a kaina kawai ka mayar da abin wasa. Mataki ma ban gama d'auka a kanta ba wallahi muddin ba ta fita daga rayuwata ba."
Ya rungumo kafada jikinsa yana dan rawa har yana gyara mini sar'kar wuyana ya ce." Ni ban d'auki maganganunta da muhimmanci ba saboda nasan wacece ke, nasan ta fadi haka ne domin ta 'bata miki rai da kishi irin naku na mata me yasa maganarta za ta dame ni tunda na fi kowa sanin da

baiwar da Allah ya yi mini na rabauta dake giwar mata shige mu zauna mu yi magana wadda za ta kawo mana sasanci.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700...VIA 0542382124.... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*154*
Ganin yana neman wuce makad'i da rawa ya sanya na tankwa'be hannunsa ya sake mayarwa tare da tarairayoni jikinsa sosai na yi 'kokari wajan 'kin barin abinda yake yi mini ya yi tasiri a tare da ni muka zauna gefan gado a tare yana ta sauke wata irin ajiyar zuciya wadda na kasa tantance ko ta mecece. Raina a b'ace na zura masa ido domin sauraran abinda zai fad'a abinda na sake kud'irewa a raina shine ko sama da 'kasa za ta had'e ba zan zauna da Hauwa ba tunda ba tare a ka hallice mu ba.  A wannan karon na shirya sosai koda Hajja za ta sanya bakinta ba ni tsammanin za ta sake samun wannan alfarmar.
Sai da ya daidaita kansa sosai ya furta." Za mu yi kwana biyu da Hauwa anan zuwa jibi zamu tafi tare da ita da yaran gabad'aya ba dai akan maganar raba gida kike magana." Ya fad'a yana kallona.
Na gyad'a kaina ba tare da na ce komai ba. Ya sake sauke ajiyar zuciya yana ce wa." Za a yi yadda ki ke so amma ya zama dole kema ki bi umarnina tunda kin san bai zai yiwu ki zauna anan ba mu muna can
 kuma duk wasu d'abiu da ki ke yi a yanzu ki ajiye a gefe ba zai yuwu ki dinga juya ni ba Amina kin san dai ba ki isa ki kafa mini doka na bi ba ko?"
Ta'be bakina na yi tare da juyar da kaina gefe wai ban isa na kafa doka ya bi ba. Ita din yake bi ai a yanzu na tu'ke tunda bai san alheri ba. Dole ne aka ce na zauna da wata Allah Ya gama hore masa ta ko'ina idan ya'ki raba ma mazauni bai shirya kashe rikici ba.
Ya juyo da fuskata yana fad'in." Ki kalle ni mu yi magana domin  fahimtar juna nake so mu yi ni dake saboda na gaji da wannan halin da ki ke yi mini ina ce akan an bani auran wannan yarinyar ne Hajara ki ka canza gabad'aya ni fa ba yaro ba ne giwa  na baki shekaru sama da goma sha biyar duk yadda ki ka kai ga gogewa na fi ki kuma bai wai ina tsoronki ba ne."
Na dube shi sosai ina cewa." Ni dama na ce ka ji tsorona ne? Wallahi ka ji tsoron Allah a cikin dukkanin lamarinka ka dinga gaskiya yanzu ba ka ji kunyar duban idona ka dinga fad'a mini irin haka ba me yasa ka ke da mance alheri ."

Ya ce." Ni kin d'auke ni mak'aryaci kenan."
Can k'asa na ce."  Iyi."
Ya sake sanya hannunsa ya juyo da fuskata yana ta'ba le'bena kafin ya furta." Ni ki ke yi wa Allah Ya isa Amina."
Na cire hannunsa ganin kamar yana so ya shagaltar da ni, na ce." Don Allah ni ka rabu da ni babu fa wani kalami da za ka yi mini na ji dad'i tunda ka rasa

Hajara sai ka nemi wata ba yanzu na ji kana waya da abokinka ba ya baka kanwar amaryarsa sai ku yi anko ina ruwana."
Ya girgiza kansa yana cewa." Ko zan yi aure anan gaba sai da amincewarki ke za ki duba mini wadda ta dace."
Na kalle shi a sakarce wai shi dole sai ya yaudareni da kalaman bakinsa. Na ce." Ya ake ciki ne za ka d'auki Hauwa ka mayar da ita can gidan Hajja ne domin fa hakan shine samun nutsuwarmu da ni da kai da ita gabad'aya."
Ya yi d'an shiru kafin ya matso ni sosai yana fad'in." Dambatta fa aka ce Amina da tafiya sosai ki bar ta ta kwana na ce miki."
Ya fad'a yana d'ora fuskarsa tsakanin wuyana. Gabad'aya ya rikice kuma na gane abinda yake so. Na cire jikina ina fad'in." Shikkenan ta kwana daya zan mata wannan alfarmar amma wallahi daga wannan kwanan ba za ta sake yi mini wani ba."
Can k'asa ya ce." Na ji abinda ki ka ce."
Ya sanya hannuwansa ya kewaye 'kuguna jikinsa na rawa.
Tsaki na ja wanda ban san lokacin da ya fito ba. Ya dago yana kallona idonsa ya canza gabad'aya ya ce." Kin san na tsani wannan dabi'ar ko. Kin ce a bi ra'ayinki an bi me yasa kike wulakantani ne Amina."
Jikina ya d'an yi sanyi jin muryarsa har tana d'an rawa bai ba ni tausayi ba ko kad'an saboda nasan akan abinda ya sanya shi rawar murya din duk yanayi ne domin ya yaudare ni ya more ni kuma Hauwa ta ci ribar abinda ta shirya domin dai ban yarda da cewa Hajja ce ta turo ta mu kwana tare ba.
Na ce." Game da kudin sadakin Hajara nawa ka ba su?"
Shiru ya yi mini yana girgiza kansa tabbacin ya kai 'kololuwa wajan Jin haushin tsakin da na yi masa wanda ni ma ban san lokacin da ya fita ba tsabar haushinsa da nake ji ne.
Na sake maimaitawa ya ce." Ban sani ba."
Na ce ." Ya asalin baka sani ba, ka fad'a don Allah a baka hak'kinka ai ba lefi ba ne."
Ya ce." Ba zan fad'a ba Amina ke kina jin kin yi k'arfin da za ki nuna mini wani abu ne.''
Na ce." A a wace ni idan da irinku a wuri ban isa ba kawai dai ina so mu biya ka hakkinka ne saboda kada nan gaba a yi mini gori."
Ya yi shiru bai tanka mini ba can kuma ya ce." Yanzu za ki ba ni ha'kkina ko kuwa?"
Na ce." Wane hakki?" don har ga Allah ban zanci hakkin kwanciya yake nufi ba ."
Ya d'ora duka hannuwansa biyu saman kirjina yana fad'in." Wannan dai mallakina ne ke kan ki ba ki da karfin ikon da nake da shi a kansa. Idan na d'ora hannu a kai ki tankwa'be kina neman rahamar Allah kuwa?"
Ya fad'a yana dam'kar d'aya da k'arfi cikin mugunta gasu tubarkallq sun sake kumburi dalilin abinda nake d'auke dashi sun cika sosai.
Na sake tankwa'be hannun ina fad'in." Allah Ya hallice ni da abina a jiki ka ce ka fi ni iko da shi abincin yarana ne masu zuwa."
Ya kuwa gigice yana fad'in." Abincin mu dai, wallahi ba ki isa ba, abincinmu ne da ni da su."

Na juya da kaina gefe ya matso ni sosai yana yi mini magana. Na girgiza kaina tare da cewa." Ba zai yiwu ba sai Hauwa ta tafi ka yi hakuri ni tunda cikin nan ma ya tsufa na daina jin wani abu

Ya ce." Ni kuwa a cikinta nake koyaushe kin matse ni da yawa Amina ba kya gudun hakkina ya kama ki uhum! mu d'an yi soyayya kad'an kafin Hauwa ta shigo sai mu kwana tare kada ta ce ba a yi mata daidai ba."

Na ce." To bari kawai idan ta shigo sai ku yi soyayyar gabad'aya."

Ya sake rikicewa yana cewa." Ya ki ka tsara yanda zai kasance."

Na rasa da wane mizani zan auna maganarsa. Ya na tsara yanda zai kasance me yake nufi. Na gane kawai a rikice yake maganarma ya fad'e ta ne cikin rashin hayyaci.

Ina sane na 'kyale shi ya dinga abinda yake so ba don komai ba sai don na nuna mata cewa kowace mace da irin tata kissar. Gidana kuma ta zo sai abinda ta gani.

Wajan sha biyu da wani abu muka sauko kasan ni da shi bayan ya samu gamsuwa da abinda ya buk'ata. Yaran sun yi bacci duka a saman kujera tana zaune zuru da tibi a kunne duk ta muzanta ganin sakkowarmu ta yi kasa da kanta fuskata a had'e kamar ma kuka ta yi.

Na wuce d'akina ban tsaya a falon ba na ji yana cawa da ita." Tashi yaran su je su kwanta. Amina bude musu daya d'akin, shi Khalil ya zo mu kwana tare a d'akina."

Dakinsu Baba Tabawa da Yusra kenan anan suke kwana na bud'e kamar yadda ya buk'ata. Ita da shi suka fara tashin yaran. Na yi shigewata d'aki a raina ina fad'in." Ki zauna da ni a gida daya ki zama 'yar aikina Hauwa, zan kuma ga abinda gobe za ta haifar ni daku ne gabad'aya.

Na rufe kofa tare da cire kayan jiki na sanya na bacci na yi kwanciyata ban sake sanin wainar da suka toya ba ba. Da asuba gari ya d'an fara haske ina saman dadduma ya shigo ya jira na kammala muka shafa addu'a a tare. Na gaishe shi babu sakewa na ce." Zan je gidanmu idan an jima zan kuma tafi da yara."

Ya yi d'an jim kafin ya ce." Babu damuwa amma ya za a yi da abin kari kada su tashi a bacci ko."

Na ce." Za ka iya bayarwa a sayo abinda za su ci ba ni jin zan shiga kicin gaskiya wanka zan yi na shirya."

Ya ce." Wace banzar magana ce wannan Amina ni zan sayi abinci bayan ina da shi a gidana, ban yi wannan lalacewar ba."

A takaice na ce." To sai ka shiga kicin din ka yi da kanka kada dai ta shigar mini kicin."

Ya dinga kallona cike da takaici ya ce." Jiya ba na gaya miki cewa zan raba muku gidan ba me yasa kike da neman fitina ne Amina. Ya kamata duk abinda ki ke ji a ranki ki ajiye a gefe mu fahimci juna gabad'aya mu gyara kuskuranmu Hauwa bakuwa ce anan gidan."

Na ce." Bakuwarka dai ai ni ban gayyace ta ba."

Ya sake had'e rai yana fad'in." Kina yin abubuwan da suke nema su wuce gona da iri fa. Ko babu

Na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

dangantaka ta aure a tsakanina da yarinyar akwai dangantaka ta jini sannan uwar yarana ce kiyayyar ki a kanta ta tsananta."
"Humm kawai na ce tare da tashi na bar shi zaune bandaki na shiga. Koda na fito baya d'akin na yi tsaki cikin raina na fara shirya jikina zuciyata cike da abubuwa ma su yawa.
Wajan takwas na fito falon yaran sun shirya ko ita ta yi musu wanka oho suna zaune a falo gabad'aya har da Baban nasu ita tana kicin domin fitowata na ji kamshin k'wai na tashi raina ya baci sosai. amma sai na daure na cigaba da amsa gaisuwar da suke jero mini. Shi kuma ya zura mini ido da alamar na gaji da wannan abubuwan da suke faruwa. Kai tsaye kicin din na nufa na same ta tana soya dankali da k'wai ta d'ora ruwan tea yana ta k'amshi citta da kaninfari.
Na cika da mamakin karfin halinta. Kai tsaye gas din na kashe ta yi sakato tana kallona. Na furta." Ba ki da hurumin yi mini yadda ki ke so a gidana Hauwa ko ni na gayyato ki ne, me ya sa za ki shigo mini kicin har ki saki jiki kina soye-soye."
Ta d'an yi murmushi tana fad'in." Amina manya ai kya bari mu gaisa ko?"
Na ce." Dube ni nan Hauwa ba ni buk'atar gaisuwar na ce miki tambayarki nake dalilin da ya sanya ki shigo mini kicin."
Ta yi 'yar dariya cikin raini ta ce. " To Hajiya masu gida ki goya ki kai gidanku."
Ta ajiye cokalin hannunta ta kama hanyar fita zalo-zalo na ce." Sakarai kawai."
Ta juyo a fusace tana cewa." Amina ai ba a sakarai d'aya sai dai sakarkaru biyu."
Na ce." Hakane da ke da ta Bauchi ko?"
Ta zura mini ido da matsanancin mamaki tasan dai inna Uwani nake nufi
Sai ta rushe da kuka mai karfi." Amina ni ke zagi, inna Uwani ce sakarai mahaifiyata." Ta fadi maganar a daidai lokacin da ya shigo kicin din ta dinga wani irin kuka hawaye na kasa tsere a kumatunta.
Yana tambayarta ta yi shiru ta kasa magana ta jingina jikin wardrobe. Can ya juyo kaina ganin yadda fuskata take ya sanya shi fad'in." Me ya faru ke ba kya jin magana da rarrashi ko?"
Na ce." Ni na ce Hauwa ta zo gidana?" Na katse shi ta hanyar yi masa wannan tambayar.
Ya ce." Gidanki ne ko nawa?"
"Gidanka ne amma kaima na fi ka iko dashi wallahi duk zan iya da ku."
Ya gyad'a kansa kamar zai rushe da ihu ya ja hannunta suka fita bata sake tanka mini ba tunda ya shigo sai ta yi shiru kawai tana kuka. Wai na goya gidan na kai shi gidanmu. Magana ta gaya mini a fakaice ashe babu dadi. Ita da uwarta duka sakarkaru ne na fad'in su yi yadda za su yi da ni.
Na same su gabad'aya har yaran sun tsuru-tsuru na wuce daki ban sake kallonsu ba.

Muna waya da Usaini ya shigo da wani irin b'acin rai a tare da shi ya cire wayar daga kunnena ya sanya a aljihunsa. Na zuba masa ido babu fargaba domin nasan ta gaya masa na ce da mahaifiyarta sakarya.

"Tunda ki ka iya zagin Inna Uwani Amina za ki iya zagin mahaifiyata yanzu kin kyauta kenan abinda ki ka yi daidai ne mace ta zo gidanki ki yi mata irin wannan cin zarafin iyaye fa aka ce miki duk iyashegen da ki ke ji da shi ina fa da yadda zan yi a kanki na kyale ki ne ganin kina da juna biyu ba ni tsoron kowa mace ni nan da ki ka gan ni sai mahaifiyata."
Ya fad'i maganar kamar gaske da 'kumaji  har da zare mini ido. A raina na ce a banza ai ba zaka iya fad'an ba Alhaji.
Na dube shi sosai tare da fad'in." Da farko daka tambaye ni maganar abin kari ban munafurceka ba na ce a a ba zan yi ba, akwai masu yin abinci a gari ka bada kudi a sayo musu mai yasa za ka ce ta shige mini kicin ko ajiya ta yi mini ne?"
Ya rasa abinda zai ce mini can kuma ya gyad'a kansa yana fad'in." Tunda kuke rashin hankalinku ban ta'ba jin lokacin da Hauwa ta zagi wani naki ba abin ya wuce kaina ya tsallaka iyaye kuma duk lalacewar inna Uwani ai idan da mutunci da sanin daraja uwace  a wajenki."
Na ce." Tunda haka ta gaya maka  na zage ta mu tafi a haka kawai idan kalmar sakarai ce zagi to zan sake maimaitawa ai iyaye ba su fi iyaye ba."
Jikinsa ya yi sanyi sosai ya juya ya fita bai sake yin wata magana ba.
Na d'auki kusan minti ashirin kafin na fito cikin shiri na same su still a falon suna shan tea har da bread tare da dankalin da ta soya musu. Minal ta ta so a guje ta rike ni tunda ta ga alamar fita zan yi. Twins din suka biyota.
Ba ni son d'aukar musu yarinya nawa biyu kadai zan yi gaba da su ba kuma zan dawo cikin gidan ba muddin Hauwa na cikinsa.
Ya yi mana shiru bai ce komai ba.
Na ce da Minal din ta je ta d'auko mini bread din da take ci. Wayo na yi mata ta kuwa juya baya da sauri nan na ri'ke hannun Usai Hassana ta biyo bayana muka fita na ja kofar da k'arfi daidai lokacin da na ji ta fasa ihu da karfin gaske.
Ayuba ya fito da mota muna ko'karin shiga ya fito da yarinyar ta yi wurjajan da kuka da majina yana goge mata da tissue.
Kamar kurma ya saka ta a cikin mota kusa da 'yan uwanta ya juya bai ce mini komai ba. Sai da na shiga motar tukkuna na tuna da wayata a hannunsa na ce Hassana ta je ta kar'bo mini jim kad'an sai ga ta da wayar a hannunta, ta shigo ta zauna suna cike da murna za su fita Ayuba ya ja motar muka fita daga gate din gidan.
Ashiru k'aramin kaninmu yana ko'karin bud'e kwantenarsa ya tsaya yana kallon fitowarmu daga mota da yake har kofar gida Ayuba ya ajiyemu
Ya taho daa sauri kuwa yana washe baki "anti Amina sannu da zuwa."
Na amsa a tak'aice ina bawa Ayuba amsa yana tambayata da kamar k'arfe nawa zai dawo ya dauke ni na ce." Ya bari zan kira shi tukkuna.
Muka nufi gidan tare da shi yana ri'ke da hannun Usaina yana fad'in." Anti sun girma sosai ban taba ganinsu ba sai a hoto."

Na ce." Kai ma ai ka girma Ashiru ka zama saurayi ina rigimar abincin hantsi.?"
Da yake yana yaro dan rigima ne idan an sha koko da safe wajan goma zai dasa rigima abinci ka'ida ne ko ba a ajiyewa kowa dumame ba shi sai an ajiye masa idan ma ba su dashi ni nake bashi ko na yi masa sabo. Idan sun dawo daga makarantar allo ba a gama na rana ba ya yi ta kuka har sai an sauke na rana sannan gidan za a samu lafiya.
Ya yi ta dariya kuwa domin ko ya mance wasu abubuwan da ya dinga yi tabbas ba zai mance wasu ba. Ya bude mini kwantenar tasa cike da kayan masarufi awo ne kadai ba ya yi ina ta dubawa ina jin dadi ganin yadda yaro ya zama manemi shi bai yi fitinar su Kamalu da Saminu ba sai da kukan kuruciya. Na ce." Aikuwa ni ma zan sanya hannuna a ciki Ashiru ya kamata a ce harkar nan an fad'ad'ata."
Ya dinga washe baki yana fad'in." Wallahi kuwa anti Amina Babanmu ne ya fara ba ni dubu dari da hamsin na fara a hankali a hankali Yayanmu Usaini ya sake ba ni dubu dari." Na ce." Ya yi daidai Hakan ni ma zan bada gudumuwata in sha Allahu."
Muka shiga ciki shiru Ina ta sallama. Can Ummansu ta amsa ya ce." Ummansu Hadiza wata'kila bacci take yi domin kwana biyu ta yi fama da mura da zazza'bi.
Ta dago labule ganina sai ta kama dariya. Na sauke ajiyar zuciya ganin yadda ta marabceta ni dama ina ta tararrabin kada ta kawo mana tangard'a a cikin lamarin nan amma yanzu yadda na hangi sukuni da annashuwa a fuskarta ya sanya na kori shakkun da nake yi. Ta  fara fadin." Maraba lale Hajiya Amina sannu da zuwa ashe tare kike tafe da yaran bakid'aya yanzu nan mutumin naki ya fita kasuwa amma ya ce idan ya gama d'aure wasu kayan da zai tura Ghana zai dawo ."
Na ce." Allah sarki babu damuwa dama ai zuwan na ki ne bari na shiga mu gaisa da Ummansu Hadiza na fito."
Tana cike da matsanancin farinciki ta ce." To shikkenan."

Na same ta a kwance a katifa shiru kamar ta rushe da ihu domin yanayin fuskata kadai ka duba za ka gane a cikin damuwa da take da b'acin rai.
Ta tashi zaune tana yar dariya "Amina maraba lale marhabun ai jiya babanku yake gaya mana kina tafe maraba." Ta sake fad'in haka tana janyo hannun Usaina tana cewa." Biyu sun girma sun zama 'yan mata."
Na zauna saman daddumar da ta shimfida mini ita kuma ta janyo yaran suka hau katifar da take zaune suna jereran gaisheta. Ta dubi Minal tana cewa " 'Kanwarsu ce wanann ko don na ga hangi kama."
Na ce." Eh mai sunana ba Amina ce muna kiranta da Minal."
Ta ce." Ma sha Allah duka gasunan sun yi wayo sosai wallahi."
Na yi murmushi ina nazartata ta d'an rame gaskiya ba kamar lokacin da suka je gaisuwar Hajiya Maryam ba ramar da ta yi yanzu ta fi muni domin kallo daya na yi mata da na shigo na tabbatar da cewa." depression yana damunta.......✍
*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700...0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*155*
Ta ba ni tausayi sosai to ya za a yi ne shiyasa ake fad'in idan kasan farkon ka baka san karshenka ba. Kuma duk wanda ya shuka alheri shi zai gani kuma idan sharri ma ka shuka to tabbas shi za ka girba da wayo na ba zan manta da irin azabar da matar nan ta gana mini ba. Na ci wahala ainun a hannunta wankin yaranta ni ce girki da cefane shara da wanke-wanke duk ni ce ba ni da sabulun wanka a gidan balle na wanki haka za ta tura Hadiza gidan kisto da kudi a yi mata ni nawa kan ya yi sama da sati hud'u ban tsefe ba idan zan ari kibiya a wajenta na dinga ra'be-ra'be kenan har sai da Gwaggo ta fahimta. Wando pant da siket kuwa sai da ya kasance biyu gare ni duk sun yayyage haka nake sanyawa a jikina nan ma gwaggon ta ankara ta sayo mini ita da Yaya Aminu da Sahura sun taimaka mini k'warai a wancan lokacin. Na yi girki da hannuna ta zo ta raba ta cikawa yaranta kwano ni ta bar mini 'kasan tunkuya duk ranar da ta tauna tsakuwa a shinkafa kuwa ina shan zagi a gidan. Sai da Ummansu Saminu ta zo gidan na fara samun sau'ki amma zahiri Ummansu Hadiza ta wahalar da rayuwata babu abinda yake bibiyarta sai hakki.
Ta dinga kuka haka kawai tana kallona na yi na yi da ita ta yi shiru ta yi mini bayanin abinda yake damunta da kyar cikin dashewar murya ta furta."Hankalina ya'ki kwanciya Amina kullum Hadiza tana raina da wannan zaman da take  a wannan waje gwara su yanke mata hukuncin ta san matsayinta, ni ma hankalina zai fi kwanciya. Da yawa mutane sai su dinga fad'in na kwantar da hankalina wallahi ba zan iya ba domin ko bacci bana iya yi sai ciwon kai."
Na ce." Ai ha'kuri da tawakalli ya zama dole Umma ki bar wa Allah lamarinsa domin Ubangiji yana so ya jarrabeka ka yi hakuri ki dinga yi mata addu'a idan da rabon za ta fito ta sake wata rayuwar sai ki ga dalilin wani lamari ta fito mun cigaba da rayuwa tare. Idan kin tsananta ciwo zai iya kama ki, kuma yana da kyau mu sake komawa asibiti tunda kin ce kina fama da ciwon kai."
Ta gyad'a kanta tana fad'in." Shine abinda ya fi damuna yanzu."
Na ce." To shikkenan in sha Allahu da kaina ma zan kai ki asibitin."
Ta ce." Na gode sosai Amina."
Shiru ya d'an ratsa wurin na dubi agogon da yake daure a hannuna sha daya saura na yun'kura da kyar na tashi sai a lokacin ta lura da cikin jikina ta ce." Ashe da sai dai mu ji haihuwa Amina haka ki ka yi nauyi."
Yar dariya na yi kawai dama sai mai kurrula ne zai gane akwai ciki a jikina dalili duk ya bi kirjina daga 'kasa ya sake bud'e ni na yi fadi sosai sai dai yayi mini mugun nauyi a mara sosai.

Ta ce."Allah Ya sauke lafiya." Na amsa da Amin a takaice. Hanyar fita na kama ina fad'in" Bari na shiga wajan Ummansu Saminu. " Ta yi shiru ba ta ce komai ba yaran suka biyo bayana na ji tana fad'in." Ba za ku zauna anan ba." Babu wanda ya waiwayeta suka biyo ni. Ummansu Saminu na zaune cikin annashuwa har da sanya sabon d'inki ta cokala d'aurin d'ankwali tana tauna cigum cike da nishadi. Mamaki ya kama ni kamar an fara hidimar bikin ita tun yau ta fara kwalliya kenan. Na zauna ina nazarinta dama d'akin gabad'aya

Rumfarta makad'e da kafet mai taushi da sabbin labulaye da sabon agogon bango sakamakon na Ummansu Hadiza da ba a sabunta shi da komai ba. Wala'ala ita ta yi gyaranta ko kuma shi Usainin ya yi mata saboda taron bikin da zai gudana. Jikina ya yi sanyi sosai wato ita duniyar nan juyawa take yi amma kuma ga dukkanin alamu zaman ha'kuri Ummansu Hadiza take yi a gidan alamu sun nuna Ummansu Saminu itace mai hutawa dalilin yaranta duka maza ne kuma sun tashi suna nema ita kuma Ummansu Hadiza ga yadda rayuwa ta juya mata shiyasa ake so mutum ya shuka alheri domin ba a san inda rayuwa za ta juya ba. Ban yarda mun yi wata magana da ta shafi abinda ya kawo ni ba sai da na kira Ummansu Hadiza domin kada abin ya yi mata yawa kuma lallai idan Usaini ne ya yi wa mahaifiyarsa wannan gyaran bai had'a da Ummansu Hadiza ba to bai kyauta ba. Gabad'aya ma gidan zan sanya a yi masa fenti da sabon simitin tsakargida a canza musu kofofi da tagogi dole ne abin ya yi mata yawa ta auri zaman d'aki kunci da damuwar yadda rayuwa ta juya mata ya janyo mata ciwon kai.

Ta kuwa ji dadin yadda na sanyota cikin lamarin hakan ya nuna mini cewa Ummansu Saminu iyakarta take nuna mata akan sabgar.

Ban yadda na gaya musu ga yadda al'amarin ya kasance har auran ya juya kan Usaini ba bayanin da na yi Babanmu haka suma na yi musu cewa yarinyar a can k'auyensu mijina take wato bunkure kuma na je naga gidansu da mahaifinta fitaccen malamin addinin musulunci ne.

Ummansu Hadiza ta saki jikinta sosai muna ta hira yayin da ita kuma Ummansu Saminu na fahimci hakan bai yi mata dadi ba sai ma ta tashi tana fad'in bari ta d'ora abinci.

Ta shigo bayan fitarta da kamar minti goma tana fad'in." Hadari ne a garin nan fa wata'kila yau mu samu ruwa." Ummansu Hadiza da sauri ta ce." Allah Ya sa ai kwana biyu mun sha zafi."

Ta share ta ba tace komai ba ta d'auki wani dan bokiti ta fita. Na dube ta a sanyaye sai ta ba ni tausayi kad'an wato abinda ta yi wa Mamanmu a can baya ne yanzu take ganin sakamako.

Ban ji dadin irin wannan zaman da suke yi ba ai na d'auka sun girma masu yi wa wasu fad'a ne ni kaina abinda yake faruwa tsakanina da Hauwa baya yi mini dadi ko kad'an don dai babu yadda zan yi ne, amma babu abinda ya fi zaman lafiya dad'i Ubangiji Allah ka ba mu ikon zama da kowa lafiya kada mu cutar da wani domin shi sharri d'an aike ne.

Hadarin ya taso sosai iska ta fara tashi garin ya turnuke farkon damuna muke ciki ga dukkanin alamu za a samu ruwan sama da wuri

Yaran suna tsakargida suna wasa sun samu sake da yake tsakargidanmu akwai yalwa na ji Ummansu Saminu tana fad'in." Ina Gambon  taku take ne ko dai ta fita."
Ummansu Hadiza ta leka tsakargidan daidai lokacin da Usaina take k'walawa Minal kira bata gidan da gaske fita ta yi gabad'aya ba mu ankara ba, suma yaran da suke wasa tare ba su  lura da lokacin da fice ba.

Na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Na tashi da kiran sunan Allah gabana na fad'uwa hijab dina na zura dalili na cire shi jin abinda jikina ya kasa d'auka zafi sosai da kyaikyayin jiki ban sani ba ko dan na jima ina rayuwa cikin ac ne oho amma dai yau yini guda duk na burkice dalilin hadarin da ya had'o da kuma zafin da ake tsugawa.
Muka fita tare da Ummansu Hadiza ma'kota ta dinga shishshiga ni kuma na fara duba yara da suke wasa a layin ban hangi rigar Minal ba.
Kafafuna suka dinga kyarma. Ashiru ya rufe kwantena ya bazama.
Kasa cire kafata na yi na koma soro na tsaya ina kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! Twins kuwa da suka fahimci Minal 'bata ta yi sai kuka Hassana tana fad'in." Kuma bata da lafiya ko Usai."
Ta daga kanta tare da zura yatsa a baki tana tsotsa hawaye na fita.
Na sake karyewa k'warai da gaske tsautsayi ne ya sanya ni taho da yarinyar nan, na tabbatar da cewa idan ba a ganta ba daga nan zuwa dare ubanta da uwarta dole su ji a wannan ga'bar da muke ciki da ni da su na rashin samun daidaito bai zama lallai su yi mini uzuri cewa tsautsayi ne ba. Za a ce me yasa nawa yaran ban sake sun fita sun shiga lungunan da ba su sani ba sun 'bace.
Ina nan tsaye cikin tararrabi kimanin minti ashirin Ummansu Hadiza ta dawo daga yawon shiga makota babu Minal babu dalilinta
Muka koma cikin gidan jikina a mace k'warai da gaske Ummansu Saminu ta sauke abinci ta ce." Ya kamata ki sanar da babanta Hajiya Amina."
Na zauna saman turmi a nutse ina fad'in." Bari mu jira dawowar Ashiru ba ni tsammanin yarinyar nan nisa ta yi. Ina rufe baki kuwa sai muka ji kukanta daga soro  na tashi tsaye da sauri.
Ashiru ya shigo da ita a hannunsa ta yi wujiga-wujiga ta ci kuka ta k'oshi har da tabon fad'uwa a goshinta da alamun jini kad'an
Na kar'beta da sauri ina dudduba jikinta gabana na ta fad'uwa ta ri'ke ni tamau tana shasheka ina jin Ummansu Hadiza na tambayarsa a Ina ya same ta ya ce tsallaken titi wani mutum yana yawo da ita a hannu zai nausa da ita titin tudun yola
Na zaunar da ita tare da cire mara riga jikinta da zullumi da fargaba na tube mata wando pant  na duba gabanta alhamdulillahi babu wata alama.
Ummansu Saminu ta juye ruwan da yake cikin fulas din shayi na surka na yi mata wanka ta zuba musu abinci suka ci cikin rashin dad'i ta b'ingire ta kama bacci. Na kasa cin komai saboda tashin hankali tabon da yake goshinta shine ya fi d'aga mini hankali kuma har yanzu zabura take yi. alamun a  tsorace take har yanzu.

Sai da na yi sallar la'asar tukkuna na ci abincin dafuduka ta shinkafa har da kifi da ruwan pure water. Na d'auki wayata domin kiran Ayuba ya zo ya d'auke mu na mayar musu da 'yar su. Ina laluben lambar direban shi kuma ya kira hannuna ya shiga rawa na daga ban iya cewa komai ba saboda tashin hankali sai nake ganin wata'kila labari ya riske shi abinda zuciyata take raya mini kenan duk da cewar yarinyar ba a san 'yarsa ba ce amma zuciyata ta kasa tsayuwa waje daya.
"Yanzu haka Hauwa tana Dambatta na sanya an kaita Ayuba zai zo ya d'auke ku saboda ganin garin da hadari ina fatan kin kammala uzurin da ya kai ki."
Na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." Na gama." Ya kashe wayar bai sake cewa komai ba.
Na dubi yarinyar har yanzu bacci take yi suna kusa da ita sun kasa sakin jikinsu kamar ma sun gaji da zaman gidan suna so a tafi. Ko da na tambaye su amsar da suka ba ni kenan mu tafi.
Na sauke ajiyar zuciya wadda ba zata lissafu ba. A haka na mayarwa da yarinyar kayanta dana cire mata. Ummansu Saminu ta shigo d'akin tana fad'in." Har yanzu ba ta tashi ba ko?"
Kaina kawai na iya daga mata.
 Ta d'an dubeta  cikin nazari kafin ta ce." Har yanzu a tsorace take kin ga ni duk da tana bacci jikinta rawa yake yi tana zabura wata'kila garin gudun hadari da iska ta fad'i ko wani ya gwabgeta gashi hadarin ya washe ba mu samun ruwan ba Allah sarki ai an auna arziki ma tunda ba a yi nesa da ita ba. Na lura yarinyar ta fi yan'uwanta rawar kai in ba haka duka fa suna zaune a tsakargida suna ta wasa a tare amma fitowata daga kicin na ga babu ita a wajan ta fita kuma maimakon ta tsaya a waje ta nausa.
A takaice na furta." Tsautsayi dai kawai amma sam ba da ita na yi niyyar zuwa ba wallahi Babansu ya kawo mini ita cikin mota tana kuka sai ta bi ni."
Ta gyad'a kanta tana cewa." Hakane abinda ya yi kiranta kenan da mutuwa ce ma haka za a shigo da gawarta."
Gabana ya fadi jin abinda take fad'i itafa dama can haka take ba ta tauna magana kafin ta furta gabagadi ce. Allah Ya kiyaye. Daga yau ma ba ni ba zuwa ko'ina da yarinyar duk rigimar da za ta yi kuwa balle wani tsautsayin ya faru.
Ashiru ya shigo yana gaya mini ga Ayuba can ya zo. Na ce ya d'auki yarinyar ya kaita mota. Na tashi da bismillah muka fito tare da yaran Ummansu Hadiza ta fito daga d'akinta da carbi da alama ba ta jima da idar sallah ba fad'i take yi yarinya kun zo lafiya lau za ki tafi da tabo a goshi abin nan bai yi mini dadi ba wallahi Amina Allah Ya kiyaye gaba."
Na amsa da Amin Ya Allah. Akwai gyare-gyaren da nake so a yi muku a gidan amma dai zan yi waya da Babanmu tunda  yau din bamu samu haduwa ba wata'kila ma gobe ko jibi a fara aikin saboda ba ni son a ja dogon lokaci cikin satin da za mu shiga nake so a kammala komai mu d'auko amarya ta tare a d'akinta.
Ummansu Saminu ta dago labule da sauri ta fito tsakargidan ta tsaya ba ta ji dadin yadda na tsaya muna sake tattaunawa da Ummansu Hadiza ba. Ita kuwa sai dariya take yi tana nuna farinciki a zahiri dai ko da tana jin haushi

da bakinciki ba ta fito fili ta nuna ba tana ta daurewa hakan ya kara tabbatar mini da cewa lallai ta tuba kuma duniya ta koya mata hankali sannan neman zaman lafiya da sulhu take yi a gidan.

Muka shiga mota Ayuba ya ja muka d'auki hanyar gida zuciyata cike da zullumi haka zalika ma jikina cike da rashin kwari da karsashi ban iya 'karya ba kuma ba zan fara akan wannan dalilin ba domin kuwa ko da na yi domin na kare kaina watarana abinda na rufe zai iya bayyana ga yaran nan da bakinsu ba ya yin shiru ga kuma tabo na daujewa a goshin yarinyar ko shi ya isa ya nuna aya. Don haka idan ya nemi dalili zan gaya masa. Yarinya dai ban yi niyyar zuwa ko'ina da ita ba ya kawo ta cikin mota ya ajiye tsautsayi ya kira ta ba kuma a son raina ba.
A gidan muka same shi shi kadai zaune a falo da waya a hannu alamu sun nuna dakon jiranmu yake yi.
Ayuba ya dire yarinyar a k'asa dama shi ya daukota tunda har da muka iso bata tashi ba sai yanzu ta fara wuri-wuri na ri'ke hannunta da kyau ganinmu a gida ya sanya ta d'an nutsu ya juyo yana kallonmu. Ayuba ya juya ya fita da sauri.
Kasa ce masa komai na yi na kama hanyar d'akina yaran suka nufi wajen da yake zaune babu wani kuzarin kirki a tattare da su gabad'aya.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*156*
Cikin nauyin jiki na cire hijab din jikina na zauna gefan gado har yanzu zuciyata bata samu nutsuwa ba dalili nasan lallai ne akwai abinda zai biyo bayan abinda ya faru. Zamana da minti goma ya shigo shi kadai d'akin. Muka dubi juna kafin ya furta." Da gaske ne abinda yaran nan suka fad'i."
Na gyad'a kaina tare da cewa." E, da gaske ne." Domin fad'in gaskiya shine abinda ya kamace ni." Ya yi shiru yana yi mini wani irin kallo na cigaba da cewa suna tare duk a wuri d'aya ta zame ta fita ba tare da kowa ya ankara ba.''
Ya tare ni da sauri ta hanyar fad'in." Ke kina ina har hakan ta faru?" Na ce." Ina d'aki a zaune tare da matan gidan su kuma suna tsakargida suna wasa."
Ya ce." Babu wani abu anan face sakaci da rashin kula Amina me yasa kin san cewa ba su ta'ba zuwa waje ba ki yi nesa da su. Har sai da ta 'bace ta yi nisa tukkuna duka za ku ankara da cewa ba ta gidan saboda kun shagalta gabad'aya."
Na danne haushin da ya ba ni na ce." Duk yanayin kular da zan yi a kansu idan Allah ya aiko tsautsayi babu yadda za mu yi kuma kada ka ga lefina fa yarinyar nan ban yi niyyar zuwa ko'ina da ita ba ka d'aukota ka kawo mini cikin mota. Me yasa don tsautsayi ya faru a kanta a ce ba za a yi mini uzuri ba."

Ya fusata sosai yana fad'in." Ba ki yarda da cewar rashin kula ba ne kenan. Ya za a yi ki je da yara wajan da ba su saba ba ki sake su ke kina wani waje a zaune  kuma ki ce a yi miki uzuri akan wane dalili ke ba za ki yi lefi a nuna miki kuskuranki ba kenan."
Na ce." Ba zan fasa fad'in tsautsayi ne ba. Kuma na iya kasancewa akan kowa amma abinda nake so na gaya maka akan yarinyar cewa tana da rawar kai fiye da 'yan uwanta me ya kai ta fita ta bar su tunda tare suke duka a zaune a waje daya suna wasa. Lefin ai ba nawa ba ne gabad'aya."
Ya gyada kansa yana cewa." Tunda kin ce haka wallahi babu inda za ki kara zuwa da yaran nan."
Na tare shi da sauri ina fad'in." Aikuwa ba ka isa ba kaffara ta hau kan ka."
Bai ce komai ba ya juya ya fita cike da b'acin rai.
Na ja tsaki ni ma cikin b'acin ran na tashi domin cire kayan jikina sun yi mini nauyi yamma ta yi sosai don daf ake da kiran sallar magriba. Na sanya doguwar riga cotton mara nauyi da hula na fito falon shiru ban ji motsinsu ba na yi tunanin ko suna sama tare da shi.
Kicin na shiga na dora farar taliya haka kawai nake sha'awar cin ta da manja da yaji da kifi.
Na kammala na fito still ban ji wani motsi ba d'akina na shiga na yi sallah ban sake fitowa falon ba sai da na yi Isha'i na fito babu motsinsu.
Kai tsaye saman na hau na bud'e d'akin nasa babu kowa shiru. A lokacin ne na gazgata abinda zuciyata take raya mini ya kwashe yaran ya yi gaba da su kenan.
Ga abinci na dafa har da su. Na dibi daidai yadda cikina zai d'auka na kira Ayuba na juye musu shi da masu gadi
Abincina na ci na k'oshi na samu yar nutsuwa na kira anti Yagana na gaya mata shawarwarin da na yanke ta sake
bada goyon bayanta sosai amma ba lallai ne ta samu damar zuwa bikin ba tunda tana tare da maijego ba ta yi arba'in ba.
Mun jima tare da Babanmu a waya muna magana har yana yi mini jajen 'batan Minal duk abinda na yanke na gaya masa ya yi ta sanya mini albarka har muryarsa tana rawa.
Bana tsammanin zan kira shi domin na tambayi dalili. Mu tafi a haka kawai domin neman dalilin ma zai kara masa kwarin gwiwa ne.
Hamusu na wakilita kamar yadda na gayawa Babanmu a washe garin ranar aka fara aikin gidan domin sabunta wasu abubuwan. Aikin gidan Usaini ma an cigaba da gyara bangaran amarya kamar yadda na yi masa alkawari duk dai a washe garin ranar da nake gidan namu. Da yamma sai ga Fati ta zo mini da yaranta su biyar yadda na gan su a lalace ita da yaran gabad'aya sai da tsigar jikina ta tashi Fati mai garin jiki da san girma duk ta tsiyaye yaran babu suttura ta arziki duk sun kod'e sun d'angale yaduka masu arha wanda take goyo uku da wata riga irin ta gwanjo hannun da wuyan ya yi masa yawa da wando wanda aka rage gefansa da zare da allura. Tana sauko shi daga bayanta zarni ya cika mini hanci domin dai ba ta sanya masa pampers ba ya kuma yi mata fitsari a jiki da zanin goyon gabad'aya.

Na zura mata musu ido jikina a sanyaye wai shin wace irin rayuwa muke ciki ne a yanzu ki ga mace da 'yan shakaru kad'an ta tsofe ta lalace saboda rashin kula da wahalar gidan aure.
Suka dinga bi daya bayan d'aya suna gaishe ni ina amsawa tausayinsu na tsirga mini wannan rayuwa Allah Ya saukaka mana ita sai na tuna lokacin da ubansu ya fito auran Fati Ummansu ta dinga murna tunda a lokacin yana tashen samun kudi sai dai babu arabi babu boko haka ta tsige mata makaranta duka ajinta biyu a sakandire ta ce karatun ai babu dole ta yi mata aure lokacin Babanmu sai yadda ta yi da shi.
Tana ta washe bakinta take cewa. " Daga gidanmu nake Umma ta ce ai kin zo garin ga ma abin alherin da ya faru na ce bari na kawo miki yara ku gaisa."
Cike da kulawa na ce." Kin kyauta sosai Fati na ji dad'i kuma ina fatan duka kuna lafiya ." Na tambayeta hakan kamar yadda al'ada ta gada amma a zahiri ai duk wanda zai ga Fati ya san ba ta cikin nutsuwa.
Ta yi d'an murmushi tana fad'in." Lafiya lau anti Amina."
Na dafa kafadarta ina cewa." Ki gaya mini idan da wata matsalar Fati ba ki jin dadin auran nan ko."
Ta kuwa fashe da kuka har jikinta na rawa na rugumeta sosai a jikina idona ya ciko da ruwan hawaye yaran suka yi tsuru suna kallonmu na kyaleta ta ci kukanta ta k'oshi kafin ta dago ta goge fuskarta.
Na ce." Gaya mini ko da akwai taimakon da zan iya yi miki."
Ta ja hanci tana fad'in." Babansu ya karye a kasuwa tuntuni anti ga yara a tsakaninmu ba na ma tunanin rabuwa da shi tunda lokacin da yake da shi ya yi mini kuma idan na ce zan kashe auran ban san wanda zan aura anan gaba ba kuma zan yi ta tunanin yarana zuciyata ba zata nutsu ba.amma wallahi anti Amina yunwa tana damun mu ni da yara sannan sai matsalar gidan haya wani abokinsa ya bashi shawara ya sayar da gidansa suka saro kaya karshe kudi ya narke masa duka suka lalace Bai tsira da komai ba. muna gidan haya muna shan tsangwama da gori. Anti Amina ba zan rufe miki ba yunwa ta assasawa Faruku d'auke-d'auke tun bai kai shakarun haka ba ko idan ma'kota sun aike shi ya rage kud'i ya boye. Ba ki ga yaran da yake bi ba yanzu sai na kwana uku biyar har sati ban sanya shi a idona ba. Har shaye-shaye yake yi fa anti Amina."
Ta rushe da kuka tana riruke hannuna.
Faruku shine babban yaronta ya zama saurayi yanzu domin ya girmi ma Kamalu tunda duka sun riga ni aure da haihuwa haihuwarta bakwai da biyar ta zo mini.
Na zura mata ido ina tuna abubuwan da suka shud'e a shakarun baya. Lallai Fati tana cikin jarrabawa. Ban yarda na yi magana ba sai da na daidaita kaina tukkuna na mayar da hawayen da ya ciko mini a kwarmin ido domin kara mata kwarin gwiwa na fara yi mata misali a kaina da sake jadadda mata cewa babu abinda bashi da karshe kuma dukkan tsanani yana tare da sauki.
Yanzu dai babban tashin hankali matsalar yunwa domin itace musabbabin dole kuma a magance ta idan ba haka ba d'aya bayan d'aya yaran za su d'auki hanyar da yayansu ya d'auka

Duk matsaltsalunta da ta gaya mini na gazgata domin ita dama halinta daban da na Hadiza sannan ba kasafai take biyewa Ummansu idan tana wani abin ba abinda dai ta dinga yi mini a lokacin kuruciya na rashin kunya wannan dama d'abia ce ta yaran da suke da uwa a gida mussaman idan an nuna musu su kad'ai ne 'ya'ya masu 'yanci ba kuma su samu tarbiya ba ko a wancan lokacin dama ni su Hassana ne da Usaina ne mutane na mun fi shiri da su haka duka muka dinga rayuwar a gidan to yanzu ga yadda rayuwa ta juyawa kowa.
A dai yadda take a yanzu ko bata bud'e baki ta fad'i damuwarta ba duk mai hankali zai gane cewa tana buk'atar taimako kuma ni ta burge ni sosai da ba ta yi tunanin watsar da yaranta ba. Ta yi hankali sosai saboda idan ta fito shi kansa zawarcin wata babbar jarabawa ce sannan wanene zai kula mata da wannan yaran.
Na ba su abinci suka ci suka koshi ina sake kwantar mata da hankali da bata tabbacin zan yi mata iyakacin bakin kokarina idan har ta yanke shawarar sana'ar da za ta yi zan taimaka mata da jari.
Da za ta tafi na bata dubu goma sannan na sanya Ayuba ya d'auketa a mota domin ya kaita gidanta na kuma tabbatar mata cewa idan hidimar bikin nan da za mu ta kammala zan yi mata Aiken kayan abinci.
Ta yi kuka kamar kamar me har sai da ta karya mini zuciya haka muka rabu da tsananin tausayin halin da take ciki a raina. Watarana sai labari in sha Allahu rabbi.
Ni kadai na sake kwana a gidan hakan bai dame ni sosai ba tunda dama na saba da hakan tuntuni kafin zuwan Baba Tabawa.
Mun yi waya da Hamusu yana gaya mini lefe ya hadu na ce ya kai musu can gidanmu su gani shima angon ya duba idan akwai abinda yake so ya kara a ciki to kafin ya kawo mini ni ma na gani
Mintina kad'an da gama wayarmu shi kuma ya kira na d'auka cikin ko'karin daidaita muryarta. Ya amsa sallamar da na yi na ji yana fad'in." Muna Abuja gabad'aya da yaran yau Hauwa za ta tare a gidanta akwai gidana jikin massalacin da na gina wanda Kamalu ya dinga limanci shekarun baya kin gane shi ko?"
A takaice na ce."A a." Ya furta." Yana cikin estate din na mu can gaba. Nan zata cigaba da zama ke kuma ki zauna a wanda muke ciki yanzu."

Na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Na ce." To."
Ya d'an yi shiru kafin ya ce." Idan kin kammala Uzurin bikin naki sai ki sanar da ni ko?"
Na ce." Ba ni tsammanin zan dawo ko bayan bikin sai na haihu tukkuna."
Ya yi shiru yana jina bai ce komai ba.
Na ce." Ka ji abinda na ce ko?"
Ya nisa kafin ya furta." To na ji." Ya kashe wayar bai ja maganar ba. Dariya ta su'bce mini ganin ya zama wani sukuku da shi ya daina ja'ina ni kuma na fad'i hakane kawai domin na tunzura shi tunda haihuwa da saura nan gaba

kusan wata biyu kuma ba ni haihuwa a wata tara sai na goma ya shiga nasan ya amsa ne kawai ba wai don ya amince ba sai don gudun tashin hankali da alama shiri yake nema.

****

To komai ya yi farko yana da k'arshe haka zalika duk abinda aka sanyawa rana sannu a hankali zai zo a yi a kammala mun yi bikin Usaini cike da annashuwa da walwala an yi komai cikin rufin asiri kuma duk abinda yake na al'ada an yi wa amarya. Gidanta na sanya a shirya mata shi sosai da kayan d'aki daidai gwargwado. 'yan uwan mamansa da Ummansu Hadiza Sahura ta jagorance su d'auko amarya domin ni ko kai kayan lefen ma ban samu sararin zuwa ba saboda hidima da gajiya sai da tare da kwana uku tukkuna na sanya Ayuba ya d'auke ni a mota ya kai ni gidan.
Ta rugunme ni kuwa tsam a jikinta tana murna tana fara'a irin wadda ta saba. Ita dashi Usainin duka sun ba ni mamaki ganin yadda suke jifan junansu da kallon soyayya kamar dama can suna son juna aka yi auran.
Na jima a gidan tare da su domin tun safe nake har yamma na nuna mata abubuwa da dama tare da sanya mata lambar wayata a cikin sabuwar wayar da ya sayo mata na ce duk abinda ya shige mata duhu ta kira ni ta gaya mini.
Sai da na yi magriba tukkuna na kira Ayuba ya zo ya d'auke ni. Muka yi sallama da begen juna.
Kwana biyu hankalina ya kwanta gajiya ta fara warwarewa Ayuba na bawa kudi ya sayo kayan abinci komai da komai na umarce shi zuwa gidan Fati kamar yadda na yi mata alkawari lokacin da ta zo mini.

****

To tunda muka yi waya kwanaki biyu da tafiyarsu bai sake nema ba har aka ci biki aka cinye babu wata magana da ta ratsa tsakaninmu tun bayan wadda muka yi da a k'arshe na ce masa sai na haihu nan tukkuna zan cigaba da zaman abuja. Ban fad'a da niyyar hakan ba kawai tsokana na yi niyyar yi amma ganin ya share bai ce komai ba ni ma na sake gyara zama duk da cewar dai hankalina yana kan yarana amma nasan za su samu kulawa wurinsu Baba Tabawa tunda ya d'auke Hauwa daga gidan.
Da yamma sai ga kiran Nusaiba muka gaisa sosai tana tambayata yaushe zan dawo ta zo har sau biyu sai masu aiki da yara har ta na yi mini Allah Ya sanya alheri ta ji labarin na yi biki.
Ina jin dadin yadda yarinyar take girmama ni sosai na ce mata ina nan tafe a kusa in sha Allahu. Muka yi sallama cikin mutunci.
Duk dai a daran ranar ina duba wayata sannu hankali na ga ya d'ora status ban ta'ba ganin ya d'ora hoton soyayya ba kai hotonsa ma ba d'orawa yake yi balle na iyalinsa ko na yara. Jefi jefi dai yakan d'ora abu nai muhimmanci walau bangaran business din shi ko kuma tunasarwa tun bayan katin d'aurin auransa da ya d'ora satikan da suka wuce kuma shima bai fi da minti ashirin ba ya goge a lokacin da yake cikin rashin nutsuwa kafin ya samu mafita sai

shakarun da suka wuce lokacin auransa da Hajiya Maryam nan zan ce naga hotona barkatai a status dinsa.
Sai kuma yau da ya d'ora hotona masu yawa. Na farko farko nasa ne  dana Samira Yayar Hauwa matarsa ta fari tun na kuruciya lokacin da suke soyayya. Sai kuma na Hauwa da yaranmu gabad'aya na k'arshe ita dashi ne a sabon gida aka yi musu ya rungumeta ita kuma ta zagaye hannunta a k'ugunsa suna dariya gabad'aya. 'Kasan hoton ya sanya alamar heart da farkon sunansa da na ta.......Nan da nan na ji wani tashin hankali ya yi mini dirar mikiya na nemi yawu na rasa a bakina wani kishi mashahuri ya turnuko mini. Idan ma da gayya ya yi domin ya dyaga mini hankali tabbas ya samu nasara domin lokaci guda na ji tashin hankali tunanika masu yawa suka fara bijiro mini a kaina wato suna can suna cin amarci a sabon gida har da hoto gashi nan katafaran falo wanda ya ji kaya na alfarma, da bai samu nasarar yin sabon aure ba ai gashi ya tare a sabon gida da matarsa suna sha'katawa har da rungume juna da  d'aukar hoto cikin nisha'di da annashuwa. Na ji tamkar an d'auki tabarya an rarrad'e mini kafafuna na ajiye wayar ko datar ma ban kashe ba na kwanta ina ko'karin sarrafa zuciyata dangane da yadda take hantsilawa tsabar kishi da tashin hankali. Da na ce sai na haihu zan dawo ashe hakan wata dama ce na bashi domin ya huta.
Can kasan zuciyata na ce mini kada abinda ya yi ya dame ki Amina tunda ta wannan sigar ya b'ullo ku cigaba da tafiya haka har kin manta da halinsa kenan
 idan bai sake yi miki maganar ba ki yi masa shiru bari ki haihu anan lafiya cikin 'yan uwa.
Abinda zuciyata take gaya mini kenan. Wani sashe kuma na'kin amincewa da hakan domin kuwa gabad'aya hankali da tunani na yana can idan har na bari muka ci gaba da tafiya a haka Hauwa za ta yi mini dariya buk'atarta ta biya.
'Ko dai ita ta d'auki wayar tasa ma ta dora hotonan domin tasan lallai zan ga ni." Zuciyata take sake gaya mini haka.
Na girgiza kaina ko Hauwa ba ta d'ora hotonansu ba shi ma zai iya d'orawa domin ya jefe ni cikin damuwa, tunda duk ya bi hanyoyin da zai lallasa ni bai samu sa'a ba ya biyo ta wannan sigar.
Na sake shiga Whasap din hannuna na rawa ban ma san me zan duba ba kawai sai na ga an goge hotonan ma gabad'aya babu su. Na sake shiga damuwa da nazarin hakan shine ya d'ora ko Hauwa domin ni a ka diora tunda an lura na ga ni sai aka goge wannan shine amasar, amma har yanzu tunanina ya kasa tantance mini wanda ya yi hakan a tsakaninsu.

Na jima ina addu'a samun sau'kin zuciya kafin na yi shirin kwanciya na kwanta gabad'aya ba ni jin dadi jikina da zuciyata. Kiran sa ya shigo wayata da ban kai ga kashewa ba. Na ajiye ta katse ban daga ba ya sake kira ta katse.
Ya kira ya fi sau biyar ban d'auka ba dana ji bacci yana shammatata ma sai na kashe wayar gabad'aya na yi addu'a cikin ikon Allah bacci ya d'auke ni......
✍
*GARKUWAR MATA*

*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA  0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*157*
Ko da gari ya waye ban kunna wayata ba saboda takaici zuwa yanzu na tabbatar da cewa shine ya d'ora status din saboda ya ba ni haushi kamar yadda ya yi mini a wancan karon lokacin auransa da Hajiya Maryam. Idan na ce ban ji haushi ba na yi karya abin ya ta'ba mini zuciyata sosai kuma ban sake gazgata matsanaciyar k'aunar da nake yi masa ba sai yanzu da nake ji har yanzu zuciyata ba ta daina zafi ba.
Tare muka yini da Sahura muna tattauna batutuwa masu yawa har take ba ni labarin irin saranda da sadudar da Idiris ya yi abubuwa da yawa sun kamace masa kudin da ya samu sun k'are tuntuni domin gabad'aya bai san yadda za a yi ya juya su su ru'banya ba birni ya dinga yi  da auran da babu ribar komai sai ta haihuwa. Na bata shawara sosai akan ta ajiye duk malamanta ta tallafe shi tunda har ya yi nadama ya kuma bata ha'kuri ai an riga an zama d'aya yaransu uku a tsakani don ma ba mai haihuwa ba ce da tuni sun fi haka. Na kuma ce mata a duk lokacin da matarsa ta haihu suka ba shi d'ansa ko y'arsa ta kar'ba ta ri'ke ta had'a da yaranta gabad'aya domin da d'a da dukiya ba a yi musu mugunta domin ba kasan wanda zaka mora ba. Wata'kila tsananin rabo ne ya sanya shi auran wanda idan ma ba a yi shi ta fannin da Allah da annabi ba za a iya samun rabon ta hanyar da Allah Ya haramta.
Sosai jikinta ya yi sanyi a wannan karon ba ta yi jayayya da maganata ba kuma da alama ta d'auki shawarar da na ba ta.
Sai daf da magriba muka yi sallama ta tafi. ban yi niyyar girki ba mun dai yi waya da Hamusu tun jiya da rana ya ce mini zai zo mu yi lissafi sai na ce masa ya taho mini da towo daga gidan Gwaggo shiyasa ban shiga kicin ba ko da rana ma Sahura wainar fulawa ta soya mana kayan manja da yaji muka ci cikin marmari.
Sai da na yi sallar isha'i tukkuna na kunna wayata.
A hankali ina duba wayar kimanin minti goma sha biyar ya kira na bari sai da ta katse ya sake kira tukkuna na daga nasa a kunnena na ji ya sauke ajiyar zuciya cikin taushin kalami ya kira sunana ." Na amsa da "Na'am."
Ya furta." Kina lafiya ko ya gajiya?"
Na ce." Kalau nake ina
yara?''
Ya sake sauke ajiyar zuciyar da nake jin saukarta a kunnena kamar yana gabana. Ya ce." Suna lafiya Amina me yasa ki ka kashe wayarki ne?"
A takaice na ce." Na huta gajiya ne shine dalili?"
Ya yi shiru na dan wani lokaci kafin ya ce." To shikkenan sai da safe ko na kira ne domin na ji ya ki ke."
Har zai kashe na ce." Ina son zuwa gidan Gwaggo gobe ko jibi."
Ya furta." Allah Ya tsare."

Na amsa da Amin jikina a d'an mace ganin duk abinda na ce zai amsa babu korafi."
Ya ce." Ba dai wata matsala ko?"
"Umm!" Na ce saboda na ji haushi da bai tambayeni yaushe zan koma ba.
Ya sake fad'in." Sai da safe?"
Na ce." Allah Ya ba mu alheri."
Ya kashe wayar ni ma na kashe tawa jikina gabad'aya ya mutu da abinda ya tsiro da shi wato tunda na ce sai na haihu zan koma ya daina takura mini. Sai na ji hakan bai yi mini dadi ba.
Ko da hamusu ya zo ma a daddafe mu kayi lissafin towon da ya kawo mini kad'an na ci na ajiye ragowa da safe na dumama.
Na kwanta da takaicin abinda yake faruwa. haka na tashi sukuku babu kuzari. Ruwan shayi kawai na sha sai da rana ta yi tukkuna na dumama towon. Zuwan Kamalu da Yusi shi ya d'an warwarar da ni na samu walwala ganinsu cikin tsabta da nutsuwa da kamala. Na dinga godiya ga sarki Allah da ya yi mini wannan tagomashi kowa ya dogara da k'afafunsa sai a lokacin ma nasan da abinda yake faruwa shirye shirye ya gama kammala karshen watan da muke ciki na musulunci yaron zai ta fi jami'ar musulunci ta madina bisa sahalewar uban rik'on nasu shine ya yi masa jagoranci ya kuma shirya masa tafiyar. Ban nunawa yaron cewa ban sani ba muka tafi kan cewa ai na san da tafiyar na kuma yi masa addu'a kwarai da gaske da fatan alheri.
Yini muka yi tare suka ce daga nan gidan Gwaggo suka nufa na ce su gaishe da ita sannan su sanar da ita ina tafe ni ma.
To abinda ya dinga faruwa kenan a tsakaninmu. Zai kira ni a waya kullum mu gaisa da kulawa amma fa ba ya yi mini maganar komawa sbuja zai dai ce mini yara suna kewata amma shi ba zan tantance halin da yake ciki ba tunda yana ko'karin daurewa ya nuna mini bashi da damuwa. Ni kuma takaicin abinda yake yi ya hana ni gaya masa ga ranar da zan dawo amma zahiri hankalina gabad'aya ya koma can da tunanin kada Hauwa ta samu damar yi mini dariya ko wata kafar da mutuncina zai zube.
Sati uku da bikin Usaini ya kawo mini amarya tun safe ya har yamma muna tare Hajara ta zama 'yar gari yarinya ta murmure ta kara kyau kuma ta fara koyar kwalliya irin ta 'yan birni sosai na ji dadin wannan lamari.
Muna tare har dare domin cewa ya yi sai ya taso daga kasuwa tukkuna zai zo ya d'auketa su tafi da muka yi waya ya ce mini yana gidanmu amma gashinan akan hanya.
muna hira a falo ni da ita maigidan ya shigo wannan karon tare da Ade suke. Haka kawai na tsinci kaina cikin faduwar gaba domin ban tsammaci zuwansa ba don bai gaya mini ba duk da da safe mun waya bai ce yana hanya ba.
Daga bakin kofa Ade ya gaishe ni ya juya ya fita da saurin gaske.
Ita kuwa Hajara tun kafin ya shigo cikin falon sosai ta zame daga kan kujera gwiwarta a kasa ta fara gaishe shi. Ya d'an yi jim yana kallonta kafin ya amsa ya dube ni a tsanake ya ce." Amarya ce ko?" Yadda ya fadi maganar ya tabbatar mini da cewa bai ma gama sheda ta sosai ba duk kuwa da cewa a lokacin da ake tirka-tirka auransa da ita da hotonta daya a wayarsa wanda shi ya nunawa Hajja wata'kila ya d'auketa hotone a lokacin domin ya kare

mata kallo ya ga ko ta dace da abinda ake buk'ata Allah ne dai masanin dalilin hakan.
Na saki fuskata sosai Ina fad'in." Itace ta zo gaisuwa da ban gajiya."
Ya gyada kansa da d'an murmushi a tare da shi ya ce." Ya yi kyau, ina angon naki yake?"
Ta sunkuyar da kanta kasa tana murmushi kunya take ji."
Na ce." Yanzu aka yi waya da shi yana zuwa su tafi."
Rufe bakina ke da wahala kuwa Usaini ya shigo. Ganinsa ya sanya ya risina yana fad'in." Barka da dare ya  kuwa sanya hannu ya dago shi ganin yana ko'karin tsugunawa ya dinga mika masa hannu domin su yi musabaha yaron yana nok'ewa ya'ki kar'bar hannun cikin girmamawa sai sinne kai yake shi kuma yana yi masa dariya tare da tsokanarsa ango na amarya."
Ya rike hannunsa sosai Yana fad'in." Allah Ya sanya alheri ka ji ko, ka kula na so na samu zama da kai kafin d'aurin auran Allah bai nufa ba, yanzu gashi mun had'u na yi maka murna kwarai domin ka yi dace da yarinyar arziki ka kula da amana da kuma hakkinta Ubangiji Allah Ya taya ka riko."
Ya dinga amsawa da Amin ya rabbi na gode ranka ya dad'e Allah ya saka muku da alheri Ubangiji Allah Ya biya bukatu."
Ya amsa da Amin Ya Allah babu buk'atar godiya Malam Usaini ai kai dan'uwana ne?"
Ya fad'a tare da kallona Yana cewa." Ko ba haka ba ne?"
Na gyad'a kaina jikina a d'an sanyaye na ce." Tabbas."
Usaini ya dube ni yana cewa." Anti za mu tafi sai mun yi waya Allah Ya saka da alheri."
Na yun'kura na tashi a hankali itama ta tashi na rika hannunta ina fad'in." Na gode da ziyara Hajara a gaida gida ki kuma kula da shawarwarin da na baki."
Ta ce." In sha Allahu rabbi anti."
Suka juya wajan da yake tsaye yana murmushi shima suka yi masa sallama. Ya fara laluban aljihunsa ya fito da kudi yan dubu sabbi kar da su ba su dai da yawa ba su wuce dubu ashirin ba ya mi'kawa mata yana fad'in." Ga shi a sayi jan baki da hoda." Ta'ki kar'ba da sauri ta bi bayan mijinta sai ni na kar'bi kudin na bi bayansu da sauri.
Koda na dawo cikin falon baya nan ya hau saman don haka sai na bi shi a daddafe na kàrasa hawa na same ya cire rigar jikinsa yana zaune da singeliti da dogon wando agogon hannunsa yake ko'karin cirewa.
Ya zuba mini ido har na kàrasa kusa da shi na zauna ya furta." Hajiya Giwa manya."
'Dan juyar da kaina na yi a gajarce na furta." Ya hanya amma ba ka gaya mini kana tafe ba."
Ya ce." Hakane tafiyar ta same ni bagatatan ai kin san Alhaji sammani ko mutumin nan da ya cutar da ni shekarun baya."
Na ce." Na dai ji labarinsa. Ya ce." Mahaifiyarsa ce ta rasu kin san mutanan Dambatta ne kuma tare suke da Hajja kawaye ne tun lokacin k'uruciya ni da shi kuma abokai ne na unguwa an tashi tare har dai ya zama amintaccena a wancen lokacin kafin ha'inci da son zuciya ya shiga."
Na ce." Allah sarki Ubangiji Allah Ya gafarta mata."

Ya amsa da "Amin a takaice. D'akin ya d'auki shiru na d'an wani lokaci kafin ya dube ni ya ce." Ya yara na ina fatan suna lafiya." Ya fad'a idonsa kan cikina.
Na ce." Suna nan kalau sun ce a gaisheka."
Ya saki fuska kuwa yana cewa." Ina amsawa amma ai gaisuwar iri-iri ce ko?"
Na yi shiru ban ce masa komai ba illa ido dana sanya masa ganin yadda ya kara haske fatar jikinsa ta yi kar har kumari ya yi a cikin wannan satikan da ban gan shi ba idan ba gizo idona yake yi mini ba, ban hangi wata kewa da damuwa a tare da shi ba ban sani ba ko wata ga'ba ya d'auka domin daina nuna mini so da rawar jiki. Jikina duk ya yi sanyi na kasa janye idona daga kansa iina Jin wani bala'in kishi a cikin raina sabon gida sabuwar soyayya tunda nake da shi ban ta'ba zama a gefansa bai ta'ba ni ba hannuwana suna shan mutsika idan ya rike haka zalika ya dinga sumbatar wuyana kenan yana shishshige mini yanzu da muka yi kusan sati biyu bamu ga juna ba babu wani abu na kewa da marari dana hanga a tattare da shi.
Ya furta." Bari watsa ruwa ki ba ni abinci ko?"
A takaice na ce." Ban yi girki ba." Na yi na yi na ha'kura kada na nuna jin haushin abinda yake yi na kasa jurewa. Ya ce." Ba ki yi girki ba kamar Yaya da me ki ka ciyar da ba'kin da ki ka yi?"
Na ce." Na dare ne ban yi ba dama daga gidan Gwaggo Hamusu ke kawo mini towo ba kasafai nake girkin dare ba."
Ya d'an yi jim yana kallona na wani lokaci kafin ya ce." Ko ni zan yi miki girkin ne Hajiyata."
"Idan za ka yi zan ci."
Ya ce." Zan yi kuwa yanzu jira ni na yi wanka."
Ban ce masa uffan ba ya tashi ya nufi toilet na bi shi da kallon takaici da b'acin rai.
Daidai lokacin da ya fito kira ya shiga wayarsa ya zo ya zauna da babban towel a jikinsa ya d'auki wayar sai da ya kalle ni kafin ya d'aga a sake ya amsa sallama.
Sai kuma ya yi shiru na wani lokaci kafin ya ce." To Allah Ya sawwa'ke ki samu bacci sosai ciwon kan zai yi sau'ki maganar masu aikin nan kuma ki ajiyeta yanzu abinda za a yi shine zan yi magana da Hajja anan Dambatta ba za a rasa wadda za ta taimaka miki ba, da safe idan Allah ya kai mu zamu tattaunar maganar sosai, ki kula da kan ki, Allah Ya sawwa'ke."

na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Shiru na d'an wani lokaci yana sauraranta kafin ya sauke ajiyar zuciya ya furta ." To babu damuwa sai na dawo." Daga haka sai ya kashe wayar ya ajiye saman dirowar gefan gado...
Ya sake tashi dai ya je ya d'auko basiline ya zauna da shi a hannunsa yana fad'in." Hauwa ce bata jin dadi tana mura da ciwon kai na dai fi tunanin ciki ta samu itama haka take zargi." Ya fad'i maganar yana d'an kallona.
A takaice na ce." Allah Ya sawwa'ke." Ya amsa daga haka sai d'akin ya d'auki shiru Ina kallonsa ya gama shafa basiline din ya shirya cikin jallabiya mai

yankakken hannu ya dube ni yana fad'in." Wane aikin zan yi miki a kicin Hajiya."
Da mamaki nake kallonsa ya gyad'a kansa yana cewa." Menene a ciki manzon rahama ma ya taimakawa iyalinsa ni kuma wanene ko dakan sakwara ki ka ce na yi miki a wannan dare na shirya ke ce fa."
Murmushi na yi a hankali na girgiza kaina tare da cewa." A a ka huta kawai to wai ma ka iya girkin ne?"
Ya furta." K'warai kuwa mu je kicin din naki ki ga yadda ake yi wani abin ma zan koya miki wanda ba ki iya ba."
Na ce." Lallai naga alama amma mu je din indomi kacal za ka dafa mini."
Ya ce." Ai ni ba ni cin indomi Amina da gaske kuma yunwa nake ji na d'auka zan samu abinci."
Jin ya fadi haka sai na gazgata gaskiyarsa babban abinda ya tsana zuwa gidan abinci ya jima yana fad'in tozarta kai ne ga maigidancin da yake sayan abinci a waje.
Na tashi tsaye da kyar ina fad'in." To me za ka ci sai na yi maka yanzu.'' Ya riko hannuna yana cewa." A a mu je dai kicin din tare sai mu yi aikin ko?"
Na gyad'a kaina ban sake cewa komai ba muka sauka kasan tare yana yi mini labarin yara da yadda suke hira kullum da masu aiki su Baba Tabawa. Na gama gane so yake yi mu yi maganar komawata can amma ya'ki yarda ya fito kai tsaye ya fad'a sai kame-kame yake yi.
Muka tsaya akan dafa jallof din taliya na kunna masa gas din ya d'auki tunkuya zai tari ruwa ni kuma na d'ebo kayan miya domin marka'dawa ya ciko tukunyar taf da ruwa ya d'ora kan gas din. Ina kallonsa ya rufe da murfi yana fad'in." Sai me za a yi?"
Na ce." Da wannan kurmemen ruwan za a dafa rabin taliya? Ya ce." Ya yi yawa ne?"
"Sosai kuwa kuma mai ake fara soyayya tukkuna a zuba kayan miya a soya tunda za mu yi amfani da busashen kifi idan mun gyara shi mun wanke sai mu zuba mu d'an soya tare da kayan miya nan sannan mu tsayar da ruwan sanwa."
Ya sauke tukunuwar tare da zubar da ruwan da ya mayar da ita kan gas din ya d'auki mai ya tsiya mai mugun yawa don wanda ya zuba zai yi gwangwani biyu ko fiye da haka."
Na ce." Kenan da mai za mu tsayar da ruwan taliyar ko soyayyiya za mu yi ne Allah Ya taimake ka."
Ya ce." Ana yin soyayyiya ne dama?"
Ina dariya na ce." E, amma ba ita za mu yi yanzu ba kuma mangyad'ar da ka zuba ya yi yawa.
Gabagad'i kuwa ya kai hannunsa zai sauke tukunyar da ta d'auki zafi man yana suyuwa. Ya cire a zabure ya matsa har sai da murfin tukunyar ya fadi kasan k'afafunsa. Ya rikice sosai yana duba yatsunsa.
Dariya kamar cikina zai yi ciwo na kashe gas din na jingina jikin wardrobe Ina kallonsa ina dariya sai zare ido yake yi.
Ya nuna mini yatsun yana fad'in sun toye Amina kin ga yadda suka yi jaaa ashe haka abin yake dama?"

Na ce." To kai wanene ya ce ka kama tukunya haka kawai, kuma ka ce ka iya girki ashe baka iya ba."
Ya ce." Idan hakane bayin Allah nan suna aiki Amina wanene yasan iya adadin yadda suka 'kone garin sauke tukunya."
Na d'an 'bata rai cikin shagwaba na ce." Su kadai kenan, ni ma ai ina yi maka girki."
Ya rikice kuwa ganin yanayin yadda na yi masa magana a sangarce da shagwaba ya matso ni yana cewa." Har dake mana kuna kokari gaskiya Allah Ya saka da alheri."
Na amsa da Amin a takaice tare da d'an zame jikina ina cewa." To zo ka ga yadda ake yi ko don gaba.
Ya kuwa taho ya tsaya a bayana yana murmushi na fara gudanar da aikin cikin nutsuwa yana yaba mini har da addu'a da tukwici sumba a wuya da kumatu a haka na yi masa jallof din taliya da dankali da kuma bushshen kifi ya ce a yi masa da manja ta yi kyau sosai tana k'amshi mai dad'i.
Kusan tare muka ci amma dai shine karfin cin kuma yadda ya zage ya ci da yawa ya tabbatar mini da cewa yunwa ce mai yawa a tare da shi.
Ban zaci zai iya d'auke kansa daga kaina ba a daran salin alin muka kwana bai nemi yin wata mu'amula da ni ba. Sai washe gari da rana gatse-gatse ya fara kame-kame da ya ga na'ki nuna na gane abinda yake nufi ya kamo ni wai na yi masa dabaru ta yadda zai gamsu yana tsoron ya kusance ni a haka na yi nauyi a cewarsa tausayina yake ji.
Ya fad'i hakane kawai don ya kare kansa amma shi kansa ya san babu wata dubara da take kwantar masa da buk'atarsa face sai wannan abin ya faru.
ban ma yi nisa wajan yin dabarun ba ya fice daga hayyacinsa maganar tausayi kuma sai ta kau ya fara ko'karin ganin ya samu hanyar zai mutunta kansa sai da na dinga ankarar da shi halin da nake ciki tukkuna a haka lamarin ya faru kamar wani sabon tuburarran mara hankali......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
*ZA MU KAMMALA A CIKIN SATIN SALLAH IN SHA ALLAHU*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*158*
Haka muka kasance cikin kula da juna mussaman daga b'angaransa wata sabuwar kulawa na dinga samu a wurinsa bini bini sai ya ce tausayina yake ji amma hakan ba ya hana shi da daddare ko kuma dai duk lokacin da lambarin ya bijiro masa ya kwanta da ni, a wannan gefen sai ya manta da tausayi girki kuwa bai sake cewa zai yi ba dalili ya ji babu sugar domin yatsunsa da ya kama tukunya sai da suka ruruce suka ja ruwa. Sai dai duk lokacin da zan shiga kicin zai bi bayana ina aiki yana damuna da runguma da ta'be-ta'be lamarin nasa dai kamar na sabon ango ko kuma wanda ya koyo wani sabon darasi ai soyayya ya iya babu karya kamar sabuwar balaga ba dattijo mai yawan shekaru ba.

Ranar sadakar uku ya ce na shirya mu je ya kai ni gaisuwa. Na shirya kamar yadda ya buk'ata din muka nufi dambatta a mota Ade direbansa ya ja mu.
A gidan rasuwar na samu Hajja tare da jama'a tunda shi daga waje ya tsaya sai daga baya tukkuna ya shigo gidan. Hajja ta dinga nuna ni ga jama'arta wasu sun san fuskata wasu kuma ba su san ni ba dama fadi take itace uwargidan nasa ai Amina sunanta, itace wadda aka dauro auransu a saudiya. Sai na zama abin kallo na dinga jin nauyi da kunya domin na kasa tantance kallon da yawancin jama'ar wajen ke yi mini.
Da la'asar muka fito daga gidan a kafa muka taka zuwa gidan Hajjan tunda babu nisa.
Ta sanya Iyami mai aikinta yi mini towon shinkafa miyar zogale domin dai ko kad'an na kasa cin abincin da aka ajiye mini a gidan rasuwar dafadukan shinkafa ce amma sun yi amfani da wani irin curry ya yi rabad'au dashi 'kamshin babu dad'i.
Wajan biyar iyami ta gama aiki ta kawo mini sannan Hajja ta ce ta zuba mini wani a fulas sai mu tafi dashi na huta girki.
Na kuwa ji dadin hakan sosai. Sai da na yi sallar magriba tukkuna ta fito daga cikin dakinta da turaman atamfofi guda uku manya ta miko mini tana fad'in.'' Kada na manta kar'bi wannan Amina bari na nemo leda."
Ya juya da sauri ta koma d'akin ta bar ni ina juya atamfofin tsala-tsala masu tsada.
Ta dawo da leda viva mai zurfi tana fad'in wannan ai zata d'auke kayan ko?"
Na kar'ba Ina fad'in." Eh za ta isa."
Ta zauna saman kujera tana cewa." A kar'ba da hakuri ban samu zuwa biki ba amma wannan a bawa amarya Hajara idan na sanya rana Yusi zai kai ni gidan na yini in sha Allahu."
Na sa dariya ina fad'in." Kai Hajja an yi abu ya wuce fa don Allah da kin bar atamfofinki ki dinka abinki."
Ta girgiza kanta tana murmushi ta ce." A a dama na yi niyya Amina sai ki sanya Ayuba direbanki ya kai mata ko kuma angonta ya zo ya kar'ba a ce babu yawa kuma ina yi musu fatan alheri."
Na ce." To shikkenan Hajja Allah Ya saka da alheri ya kara girma Ubangiji Allah Ya sa a fi haka, mun gode sosai."
Ta amsa da kulawa tana kallona kafin ta ce." Ya gaya miki Kamalu zai tafi karatu can Madina ko?"
Eh ya gaya mini." Na fadi haka duk da har yanzu bai ce mini komai ba.
Sai ta gyada kanta tana cewa." Ki kara yi wa yaron nan addu'a akwai alamun haske a cikin al'amarinsa in sha Allahu za a amfana dashi."
Na furta." In sha Allahu rabbi Hajja na gode Allah Ya saka da alheri."
Ta yi murmushi ba ta ce komai a daidai lokacin ne kuma ya shigo yana waya ya tsaya tsakiyar falon duk muna kallonsa har sai da ya kammala tukkuna. Ya dube ta yana fad'in." Hauwa ce ta kira waya wai Sultan baya jin dad'i."
Hajja ta ce." Ashsha me yake damunsa?''
Ya gyada kansa da Yar damuwa ya ce." Ciwon ciki abinda dai tace kenan ya kwana biyu bai yi bayan gida ba yana ta kuka uwar rainon nasa ce ta je tana gaya mata halin da yaron yake ciki amma ya sha magani a cewarta."

Hajja ta ce." Wata'kila wani abin ya ci ya dam'ke masa ciki sai an kula da abinda za a dinga ba shi ya ci mussaman abinda ya danganci madara da fulawa."
Ya furta." Sauyi ne kawai tunda yaron ya fara cin abinci bai ta'ba irin wannan ba ko ba haka ba ne?"
Ya fad'a yana kallona na ce." Sosai kuwa kuma Baba Tabawa na kula kwarai da gaske da abincin da zai ci, tana kokari a kansa gaskiya.
Ta ce." To shikkenan Allah Ya sawwa'ke ai tunda ya sha magani da sauki cikin zai saki zuwa dare sai ka kira waya ka tambayi jikin nasa."
Ya ce." Hakan za a yi in sha Allahu, ni ma ai ina tunanin jibi zan koma."
Ta gyad'a kanta tana cewa to babu lefi ai tunda an yi uku sai kowa ya koma bakin aikinsa."
Ya dube ni cikin kulawa yana fad'in." Tashi mu tafi."
Na tashi da bismillah tana fad'in." Sannu ai gwara ki zauna nan din Amina ki haihu ni kaina hankali zai fi kwanciya."
Da sauri ya ce." Ai ba sabuwar haihuwa ba ce Hajja."
Ta ce." In ji wa? au! haihuwa dama akwai sabuwa da tsohuwa ina ce idan ta yi nisa ne ma ake jin jiki, ko makaho ne ya dubi yarinyar nan ya san tana cikin ibada."
Ya yi shiru bai ce komai ba amma gabad'aya jikinsa ya yi sanyi a haka muka yi sallama ta rako ni har farfajiyar gidan lokacin shi tuni ya shige mota.
Ade ya bude mini kusa da shi na zauna da ledar atamfofin Hajara da madaidaicin fulas din  towona. Ina zama a gefansa ya kar'bi ledar ya ajiye kasan k'afafunsa saboda kayan sun yi mini yawa a hannu
 Ade ya shiga mazauninsa muka d'auki hanya.
Har muka isa gida bai yi magana ba. Ya rage walwala da nishadi ya yi shiru abinsa tabbacin akwai abinda yake damunsa.
Na daure na fara tambayarsa ko ba ya jin dadi ne ya ce dani 'kalau yake gajiya ce kawai.
Ko da na yi masa tayin towon ma kafin mu kwanta ya ce a a shayi kadai zai sha shima cikinsa ya b'aci.
Na kyale shi kawai na zauna na ci towona na koshi na sauka da kayan na dawo na same shi yana waya da Hauwa jikin yaron yake tambayarta ga yanayin fuskarsa amsar da ta ba shi ba mai dadi ba ce.
Raina ya ba ci sosai wai shin ya ma aka yi Hauwa ta san yaron ba shi da lafiya ne abinda ba tare suke ba, ba fa da gaske ba ne karya take yi ta mayar da shi shashasha tana daga masa hankali saboda ta gane lagonsa akan yara yake yau tace wannan gobe tace wancen kwanaki ta bugo waya tace bata da lafiya yau kuma ta kirkiri ciwo ta d'orawa yaro wane irin jahilci ne wannan. Ta gama gane damuwarsa akan yara shiyasa take amfani da wannan dama. Gashi muna cikin farinciki da soyayya da kulawa lallai sai ta rusa hakan ta kira shi ya dawo wajenta shine hankalina zai kwanta.
Na bude baki ina fad'in." Idan ba ka farga da wuri ba wallahi Hauwa daf take da ta mayar da kai sakarai ko ma nace ta mayar da kai tuntuni shashasha take kallonka."

Ya dube ni da b'acin rai yana cewa." Wace irin magana ce wannan Amina ana 'karyar ciwo ne?"
Na ce." Tunda ba ta da hankali ita don ta yi hakan ai ba abin mamaki ba ne, watarana za ta iya kiran ka ta ce wane ya mutu tunda jahila ce."
Ya yi sakato yana kallona ni ma ina kallonsa na ce." So take yi ka koma gare ta domin ku cigaba da cin amarci a sabon gida, na gaya maka Hauwa ba za ta ta'ba canzawa ba kuma ba zata zauna da ni tsakani da Allah ba sai ta yi mini bita da 'kulli a rayuwata me na tsare mata."
Ya yi shiru kawai yana kallona na cigaba da cewa."Ka yarda ko kada ka yarda Hauwa 'karya take yi Sultan lafiyarsa lau."
Ya ce." Na ji, ke yanzu abinda ki ka yanke a ganinki daidai ne na gaji da wannan abin da ki ke yi mini ni nake auranki ko ke ki ke aurana?"
Da mamaki a tare da ni na ce." Me kuma na yi maka yanzu, gaskiya na gaya maka na ce ka farka ka kuma yi aiki da tunani akan abinda matarka take yi."
Ya ce." Ni ba wannan ne damuwata ba so ki ke na kwanta ki taka ni shine karshen so da kulawa da tarairaya me zan yi miki kuma abinda ya rage kenan."
Sai kawai ya kwanta ruf da ciki ya mike sosai yana fad'in." Ta shi ki hau ki bi ta kaina kawai Amina, hakan zai kara tabbatar miki da cewa kin gama da ni, sai abinda ki ka gindaya mini."
Dariya ta kama ni amma na danne ban yi ba sai na kasa gane dalilin wannan rikicin da ya bijiro da shi a yanzu ban sani ba ko maganar da mahaifiyarsa ta yi a d'azu ce ta 'kara fusata shi shine ya sar'kafe maganar ya had'ota da wata a ganinsa kenan na mallake shi juya shi nake yi."
Na sassauta sosai tare da cewa." Ni dai don Allah ka tashi kada ka sanya mala'iku su tsine mini me ya yi zafi zaka kwanta kace sai na taka ka."
Ya ce." Kin san Allah ba zan tashi ba Amina sai kin bi ta kaina kin wuce hakan zai kara tabbatar miki da cewa kin gama da ni, haba don Allah na gaji wallahi rayuwarki kawai ki ka sani ni ko oho, ki tashi kawai ki yi yadda na umarce ki."
Na yi kasa'ke ina kallonsa har yanzu yana kwance ruf da ciki. Na ce." To ai kamata ya yi ka gaya mini abinda na yi maka sai na baka ha'kuri ba wai ka kwanta ka ce na taka ba, akan wane dalili."
Yana daga kwancen ya ce." Sai na gaya miki ga abinda ki ka yi ke din yarinya ce, ai duk abubuwan da ki ka jima kina aikata mini kin sani, tunda ba k'ank'anuwa ba ce."
Na yi shiru kawai ina kallonsa saboda bakina ya mutu ma gabad'aya ya juyo da fuskarsa yana kallona har yanzu babu wasa a tare da shi ya ce." Ba za ki tashi ki taka ni ba."
Na girgiza kaina a tsanake na ce."Babu halin hakan me yasa zan taka ka Allah kada ya nuna mini wannan rana."

Na kudi ne wannan littafin kada ki karanta ba tare dà kin biya ni hakkina ba.

Ya gyad'a kansa tare da tashi zaune yana fitar da numfashi sama-sama ya jima a haka kafin ya tashi ya shiga bandaki na bi shi da kallo ina girgiza kaina ya fito d'aure da alwala ya hau dadduma.

Haka muka kwana ko hannuna bai ri'ke ba. Da safe na gaishe ya amsa a dakile ya koma ya kwanta bacci ya yi sosai sai wajan sha biyu ya sakko kasa.
Lokacin na gama had'a kayan sanyawata dana ware domin aikawa da Fati na fito da akwatin kayan domin kiran Ayuba na same shi zaune shi kad'ai ya kunna tibi abinda ba dabi'arsa ba.
Ya dube ni muka kalli juna kafin ya ce." Wannan akwatin ta mecece Amina?"
Na ce." Ayuba zan aika gidan 'kanwata Fati."
Ya yi shiru bai ce komai ba yana kallona na ajiye akwatin na bud'e kofa na fita domin kiransa.
Sai da na shigo tukkuna ya biyo bayana na ce masa ya d'auki akwatin ya kai mata sannan na ya gaya mata zan kira ta a waya zuwa dare.
Bayan fitarsa na je na zauna kusa da ni bai kalle ni ba da romot a hannunsa yana duba tashar da zai k'alla.
Na matsa kusa da shi a hankali na ri'ke hannunsa ya dube ni babu yabo babu fallasa ya mayar da hankalinsa kan tibin.
Bakina nasa a kunnensa cikin k'aramin sauti na ce." Babyn love." Ya yi shiru bai ce komai ba. Na zura yatsa a kunnansa ina fad'in. " Ko ka zama kurma ne Allah Ya ja zamaninka my heart."
Ya dube ni yana lumshe idonsa a kasalance ya ce." Menene?"
Na ce." Kai ne my love dina"
"Humm!" kawai ya iya cewa kafin ya janye idonsa daga kaina ya cigaba da daddana romot.
Nasa hannuna a cikinsa ina fad'in." Yunwa kake ji fa, tun jiya baka ci komai ba ina sane gaskiya rayuwata tana cikin had'ari."
Ya dai yi shiru bai tanka mini ba, sai ma ya fara muzurai yana d'an 'bata fuska.
Na dake sosai ina fad'in." Bari na yi maka abinci ko, wane iri ka ke so na yi maka? umm ka fad'i kalar da kake so zan shirya maka yanzu."
Ya yi gyaran murya bai kalle ni ba ya ce." Tafiya zan yi gobe idan  Allah Ya kaimu."
Na ce." Na shirya kenan mu tafi tare ko?"
Ya kalle ni da sauri fuskarsa ta d'an sassauta. Sai kuma ya d'auke kansa yana cewa." Duk yadda ki ka gani Amina?"
Na ce." Farincinka shine nawa Habibi za mu tafi tare in sha Allahu."
Ya gyada kansa amma bai ce komai ba.
Na ce." Me zan yi maka fannin abinci."
Ya ce." Ki yi duk abinda ranki yake so zan ci."
Na sauke ajiyar zuciya a hankali na ce." To shikkenan in sha Allahu."
Kicin din na tashi na nufa na fara aikin cikin nutsuwa mintinta ashirin a tsakani ya biyo ni lokacin ina yanka albasa ya furta. "Kawo na taya ki ko."
Kai na girgiza tare da cewa." Ka huta kawai ba ni so ka yanke  hannunka ni zan yi komai na samu lada."
Ya tsaya daf da ni a hankali na ji yana cewa." Wane suna ne na ji kin kira ni dashi da zu." Yafad'a yayin da ya d'ora hannunsa saman kirjina.
Na d'an janye kad'an kafin na ce." Suna wane iri Allah Ya taimaki rayuwarka."

Ya girgiza kansa yana cewa." Babyn love da dad'i sunan. Me yasa tuntuni ba ki kira na da shi."
Na ce." Ka manta dai Ina kiran ka dashi mana a wani yanayi."
Ya yi shiru yana kallona har ina jin saukar ajiyar zuciyarsa. Ya ce." Na tuna a yanayin nan da ni dake muke ganin tamkar mu kadai Allah ya hallita a duniya ko."
Na gyad'a kaina ina murmushi na ce." E, amma idan kana so a cigaba da kiran ka da sunan sai a cigaba."
Ya ce." A a ki cigaba da kira na dashi a yanayin nan na mussaman ni tsoho ne idan yarana suka ji ana ce mini baby dariya za su yi."
Murmushi na yi ina fad'in." To haka za a yi kuwa."
A haka na gama shirya abincin muna hira da kalaman soyayya.
A daran Usaini ya zo ya kar'bi sa'kon matarsa na wurin Hajja.
Sannan na ce masa zan je gidan Gwaggo ya ce na shirya mu je tare shima zai gaisheta. Allah sarki Gwaggo ta ji dadin ganinmu bakinta kamar gonar audiga ta samu alheri na kudi a wajensa tana ta yi masa godiya har sai da ya gaji ya hana ta ya ce don Allah ta daina yi masa godiya akan yana rik'on yaran da addini ya bashi damar zame musu uba. Koyaushe idan magana ta tashi zai ce haifarsu ne kawai bai yi ba amma tunda yana aurena ubansu ne kuma addini ya mallaka masa.

***

Yadda na samu Sultan cikin walwala da wani irin kuzari da lafiya ya tabbatar da mini da cewa hasashena akan Hauwa gaskiya ne. Shi kansa uban dana d'auki yaron mussaman na kai masa shi d'akinsa ya d'aga shi sosai yana duba shi fadi yake yi ya k'ara nauyi sosai Amina kin ga dai duka sati daya rabona da shi amma ya yi mini girma a ido ashe Hauwa bata da hankali dama."
Shiru kawai na yi ban ce masa komai ba zuwa yanzu ai ya kamata ace ya gane halin matarsa muguwar ma'karyaciya ce mara son zaman lafiya.
Kwanana biyu da dawowa yara sun yi doki da murna haka zalika ma masu aiki aka kewaye ni ana ta farinciki na dawo na zama kamar ba'kuwa har Baban nasu ya dinga kishi yana jin haushi wai shi ba su damu da shi ba. Yadda ya hak'ikance yana fad'a abin ya yi ta ba ni da dariya.
Da daddare Salim da Adam suka shigo mun jima tare da su a falo muna hira nan Salim yake gaya mini ai yana da lambar wayar Kamalu har ya kira shi ma ya taya shi murna tafiya karatun da zai yi. Ikon Allah kenan gabad'aya yaran sun samu wata iriyar nutsuwa mussaman shi Salim din da ya canza ko maganarsa ma cikin nutsuwa kuma duk wadda zai furta mai muhimmanci ce. Lallai Allah yana kishin bayinsa ya sanya musu nutsuwa da tawakalli babu uwa babu uba, haka zalika babu 'yan uwan uwa nagartattu. Dangin Babansu ne kawai masu nagarta sai Kuma uban rikonsu a yanzu wanda ya zame musu bango. A wannan ga'bar shi kansa maigidan na sara masa domin ya yi namijin kokari kwarai da gaske duk abinda uwarsu ta yi masa na illatarwa ya ture ya rungumi yaran abokinsa domin cikashe wasiyyar da ya bar masa. Hakika ya zama uban marayu ni ce sheda tunda ni ma ga nawa nan ya

runguma har yana b'acin rai idan an yi masa godiya bisa abinda yake yi musu.

Sati daya da dawowata komai ya daidaita a gidan mun samu nutsuwa da kwanciyar hankali tun daga kan maigayyya da aiki yaran dai kaf muna tare da masu aiki muna cikin nutsuwa da walwala ba ni da damuwar komai tunda ba ni ganin gilmawarta balle ta takale ni ko ta gaya mini banzar maganarta. Ya je ya yi mata kwana biyu ya zo ya yi mini kwana biyuna haka muke yi babu canji kuma shima yana ta ko'karin ganin ya yi adalci domin dai ya nemi zaman lafiya kuma ya samu ta sashena domin ba ni da niyyar d'aga masa hankali akan komai tunda ba ni nake auranta ba abinda yake gabana a yanzu rabuwa da abinda yake cikina lafiya.
Ranar wata lahadi girkinta ne tunda gari ya waye bai shigo ba. Hakan sai ya d'an dame ni tunda bai saba da yin hakan ba yana shigo mana ya jima tare da mu a yi hira haka zalika ma ranar girkina yana zuwa gidanta ya d'auki wani lokaci kafin ya shigo mana.
Na fara nemansa a waya gashi dai tana shiga amma sai a katse na kira ya fi sau shida idan ta shiga sai a katse.
Ga yara tun safe sun tafi tahafiz sai yamma balle na tura Khalil gidan. Bai kira waya ba kuma bai shigo ba abin dai da mamaki.
Wayarsa kuma na kira ana kashe mini. Ban zarge shi kai tsaye ba sai dai zuciyata ta shiga wasi-wasi akan hakan.
Gefin magriba ya kira ni na daga da sauri na ji muryarsa a dashe don da 'kyar ma yake magana yana yi tari na sar'kafe shi yake gaya mini baya jin dadin ya tashi da mura da zazza'bi har da tari. Har da ba ni ha'kuri bai shigo ba kuma bai kira ni ba."
Gabad'aya jikina ya mutu na dinga yi masa sannu. Tabbas bai iya mura ba tunda ta ta'ba kama shi a gidana farko-farkon auranmu na yi jinyarsa.
Na ce masa idan an jima za mu shigo tare da yaran gabad'aya mu duba ka Allah Ya sawwa'ke." Ya amsa da Amin muka yi sallama.
Na zauna cikin damuwa da mamaki. Hauwa ce kenan ta dinga kashe mini waya a maimakon ta d'aga mu yi magana take ganin k'yashin yin hakan. Humm! shine yake ganin za mu zauna lafiya da ita har yanzu bai san wacece matarsa ba Gabad'aya lamarinta ni yanzu tsoro yake ba ni wallahi da jefa ni cikin fargaba. Ba ni da nufin zalintarta ko cutar da ita shiyasa ma muddin nasan ranar girkinta ne ko ya shigo wajena ba ni sakin jikina da shi balle tsautsayi ya sanya mu shiga hakkinta.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124.... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*159*
Bayan isha'i na fito cikin hijabina har k'asa kai tsaye d'akinsu Baba Tabawa na nufa, ita da Taburni suna zaune cikin fahimtar juna suna hira Sultan na

tsakiyarsu da abin wasansa yana ta wasa gefe guda kuma flat ne da abinci a ciki da alama nasa ne za ta bashi wasa ya d'auke masa hankali
Gaisawa muka sake yi kafin na ce." Sultan za a ba ni aro za mu je gabad'aya domin duba Babansu ne ba shi da lafiya yana ta fama da mura da zazza'bi."
Baba Tabawa ta ce." Subahanallahi ashe ba shi da lafiya dama?"
Na ce." Yau dai ya tashi da ciwon shiyasa ai bai shigo mun gaisa ba." Taburni cikin mutuwar jiki ta furta." Tabbas kuwa, don Allah a yi masa sannu da jiki Hajiya Allah Ya sawwa'ke."
Na amsa da Amin zan gaya masa in sha Allahu."
Muka fito daga d'akin tare da Baba tana ri'ke da yaron tana fad'in." Hajiya Amina ko dai mu je tare ne ya yi miki nauyi ga yanayin jikin naki kema Allah dai ya budi ido lafiya."
Na ce." Bari Khalil ya fito ya d'auke shi ai na ce miki tare duk za mu je da yaran."
Ta ce." To hakan ya yi. Muna tsaye yaran suka fito tare da Mairo dama kafin na shiga sallah na sanar da su. Kowacce da hijabi a wuyanta. Khalil ya fito shima na ce ya d'auki yaron. Suka yi gaba gabad'aya na bi bayansu.
Muna fita farfajiyar gidan masu hidima da gidan suka fara rige-rigen gaishe ni, ina ta amsawa da kulawa, tunda babu lefi tsakaninmu da su akwai mutunta juna sosai.
Masa'udu da yake akwai sabo a tsakanin da yaran dalili shine yake jigalar kai su makaranta
yana ta tsokanar Usaina itace mai tsotsar hannu tana hararsa tana fad'in." Na daina kai ne kake yi ai kai ka koya mini.
Ta k'aramar k'ofa muka fita gabad'aya can muka hangi mota za ta shiga gidan Momi Hajiya Maryam kenan duk da ban gane wanda yake ciki ba amma ganin motar ta tsaya ya sanya ni ma na tsaya. Adam ya fito daga cikin motar ya karaso har wajan da nake tsaye yana dariya yake ce wa." Mama ina yini, ina za ku je haka da daddare, da yaran duka?"
Ni ma cikin murmushi da kulawa na ce." Za mu duba babanku ne baya jin dad'i."
Yanayinsa gabad'aya ya canza ya furta." Ai ba mu sani ba wallahi me yake damunsa?" Ya fad'i maganar a rikice da damuwa a fuskarsa.
Cikin nutsuwa na ce." Mura ce da zazza'bi ka kwantar da hankalinka Adam ba a kwance yake ba."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Mama mura ai ciwo ne mai tsanani tunda har Annabi Muhammadu s.a.w ya yi magana akanta bari na yi magana da anti Nabila tana cikin mota na je daukota daga airport ne sai na zo mu je tare na duba shi."
Na gyad'a kaina ban ce komai ba shi kuma ya juya a gaggauce ya nufi inda motarsa take.
Mamaki nake yi ashe har yanzu Nabila na gidan tare da su. Ko da yake hakan ma ya yi daidai tunda har suka aminta da zamanta wata'kila ta fi sauran 'yan uwan maman nasu gaskiya da kuma k'aunarsu tsakani da Allah duk dai ba a tona zuciyarta an gani ba A

amma dai tsayin wata kusan takwas da rasuwar Maryam take zaune tare da su ban ta'ba jin wani k'orafi ba nasam idan da akwai matsala to tabbas Nusaiba za ta gaya mini."
Ga mamakina sai na ga sun fito daga motar tare da ita. Duk da dare ne amma akwai haske manyan fitilu mabambamta a estate din  ta hasken nake hangenta tun daga nesa a yayin da suka jero da tare da Adam din ta ci wata uwar kwalliya cikin wani lece wanda aka yi masa d'inki riga da siket matsatstsu ta k'ara ki'ba ta cika ta ko'ina d'inkin da yake jikinta ya gama bayyana hallitun jikinta tunda ba ta yi amfani da babban mayafi ba da takalmi mai tudu a kafarta wanda yake hade da wata madaidaiciyar jaka mai adon duwatsu masu kyalli. Kana dai ganinta ka ga manyan zawarawan da suka ci suka kuma tayar da kai zawarawa irin na Abuja masu kafacity amma yanayin dressing dinta ya gama bayyana cewa ba ta da mafad'i domin kuwa da da akwai shi ina ganin hakan ba zata faru ba. Irinsu na nan da yawa da suke 'batawa zawarawan da suke gefe a killace domin kare kansu.

Na janye idona a daidai lokacin da suka 'karaso wajan da muke tsaye da yaran. Cikin sakin fuska da kulawa ta furta." Hajiya Amina mun yini lafiya ya yaran duka yanzu Adam ke gaya mini Yallabai babu lafiya wallahi ni ma dawowata kenan gida sati na biyu a dubai."
Na ce." Lafiyarmu lau alhamdulillahi ya su Hanif wallahi kuwa amma da sauki ai ba akwance yake ba mura ce da zazza'bi ke damunsa.
Da yanayi na alhini irin na al'ada ta furta." Mu je ni ma sai na duba shi, Ubangiji Allah Ya kara sau'ki."
Na ce." Amin Ya Allah." Kusan tare muka jera tafiyar ni da ita. Adam ya bi yaran suka yi gaba tunda sune suka san gidan ina jinsa shima yana tsokanar Usai akan dai tsotsar hannu tana ta zum'bura ba'ki idan ya riko hannunta ta fizge ta koma gefe. Nabila sai dariya take yi tana fad'in.  Usai iya rigima kenan ashe ba ta daina tsotsar hannun nan ba."
Murmushi na yi wanda babu nisha'di a cikinsa na ce." Tukkuna dai zata daina idan girma ya zo da sauki ma a hakan ai ta rage.
Gidan bai kai wanda nake ciki girma da tsaruwa ba. Amma dai daidai gwargwado an narka masa dukiya shima tun daga wajensa zuwa cikinsa komai na iko ne falon ya tsaru da sabbin kayan more rayuwa kamar dai yadda na gani a hoton da ya d'ora.
Suna zaune shi da ita a falon tana gefansa a zaune ta yi gayu sosai cikin shadda da surfani an yi d'auri mai hawa-hawa sannan an sha yari da sarka da abin hannu.  Da yake shadda ce sai ta kara mata kumburi da kwarjini ramar ta 'buya. Yana cikin jallabiya da Loptop dinsa a gabansa gefe guda kuma fulas din shayi ne a ajiye da karamin cup a kusa da shi.
Muka shiga tare gabad'ayanmu. Ta yi wani bala'in shan kunu ta amsa sallamar sai kuma ta yi kasa da kanta.
Shi kam rufe computer ya yi ba shiri saboda yaran gabad'aya kaf wurinsa suka nufa.
"Baba sannu, Baba ina yini baba ya jikin naka?"

Abinda suke ta fad'i kenan Minal har tana ta'ba wuyansa tana cewa." Zazza'bin ma ya sauka ko?" Tana kallon fuskarsa
Yana dariya ya ce."DIN bai sauka ba tunda kun zo zai gudu garinsu.
Hassana ta ta'ba wuyansa a karo na biyu kamar yadda Minal din ta yi ta ce." Babu zafi jikin naka Baba Allah Ya ba ka sau'ki."
Ya amsa da Amin yana ri'ke hannunta, ita kuma Usaina fad'i take yi Baba maganarka wani iri kasha tomtom kaji baba!"
Na ce." Wai ba za ku samu nutsuwa ba ne haka ake duba mara lafiya?"
Suka nutsu tare da samun waje suka zauna. Khalil ya nufe shi da Sultan a hannunsa yana fad'in." Baba barka da dare ya jikinka?" Ya amsa yana cewa." Na ji sau'ki Babana." Ya mika hannunsa ya kar'bi Sultan da yake ta wangale masa
baki yana dariya da gwalantun kiran sunansa.
Khalil din ne ya fara gaisheta a hakimce ta amsa tana wani fizge kanta. Daga nan kuma yaran suka shiga gaisheta ganin yadda yayansu ya yi ta amsa tana ta'be baki.
Maganar Nabila ta katse nazarin da nake na ji tana ce wa." Allah Ya taimake ka an yini."
Ya dube ta babu yabo babu fallasa ya amsa da lafiya a takaice ya ce." Yau ki ka dawo ne?"
Ta furta." Eh wallahi dawowata kenan Adam ya d'auko ni a airport."
Ya yi shiru bai ce komai ba Adam ya shigo dama a waje muka bar shi lokacin da za mu shiga an kira shi a waya.
A nutse ya kàrasa gabansa ya durkusa har kasa yana gaishe shi ya dafa kansa yana amsawa da kulawa ya ce." Mama na gani da yaran gabad'aya ashe ba ka ji dad'i ba Ubangiji Allah Ya kara afuwa."
Ya furta." Na ji sau'ki ai tunda na sha magunguña sai dai rashin karfin jiki kuma na gode sosai Allah Ya yi muku albarka."
Ya amsa da "Amin.
Ita ta fara tashi tana d'an duban Hauwa ta ce." Madam ina yini ba mu gaisa ba."
Shiru ta yi ba ta amsa ba. Sai ma ta d'auki wayarta tana dubawa. Adam ya dinga fad'in." Ina yini tana jinsa sarai sai daga can kuma ta amsa ba tare da ta dago kanta ba.
Nabilan ta yi gaba da zummar fita kafin Adam d'in ya bi bayanta.
Falon ya rage mu kad'ai Hauwa dai ko nahiyar da nake bata kalla ba balle na samu arzikin gaisuwa abin ya ba ni dariya sosai wai ita matar gida tunda ni na zo a ganinta ni zan gaisheta.
A marairaice na ce." Ya jikin naka?"
Ya tsira mini ido cikin wani yanayi kafin." Ya furta." Ba zan ce miki komai ba giwa, wato idan zan rasu baki damu da ni ba ko?"
Ajiyar zuciya na sauke a hankali cikin 'yar shgawaba na ce." Ka duba wayarka ka ga iya adadin kiran da na yi maka gabad'aya ni da yara yini muka yi da damuwa ba ka shigo ba kuma ba ka ce za ka yi tafiya wani waje ba.

Ya lalubi wayarsa yana cewa." Wajen da ba k'asa nan ake gardamar kokawa bari na duba."
Ya shiga duba wayar yana fad'in." Ban ga kiran ki ba kin kare kan ki ne kawai."
Ya miko mini wayar yana cewa." Duba ki ga ni."
Girgiza kaina na yi a nutse na ce." A a ba sai na duba ba, amma fa babu buk'atar rantsuwa na kira ka ya kai sau bakwai da ta shiga sai a katse kiran babu matsalar network my love katse mini kiran aka dinga yi."
Ya furta." Ya ban ga alama ba."
Kai tsaye na ce." Wata'kila kai ne ka goge?"
Ya dube ta tana zaune tana jin mu da wayarta a hannu kanzil ba ta ce ba. Ya girgiza kansa tare da ajiye wayarsa a gefansa.
Shiru bai yi wata magana ba sai hayaniyar yaran Sultan tuni ya sauka daga cinyarsa ya shiga cikin 'yan uwansa.
Ya dube ni muka had'a ido sai kuma ya dube ta tana zaune gim ya d'aure dai ya furta." Gaba kuke yi ne da junanku?"
Kallonsa ta yi kafin ta ce.'' Ba dabi'ata ba ce amma tsakani da Allah Amina ba gidana ta zo ba, me ya sa take yi mini wani irin kallo, ni da naje gidanta haka na yi mata a gabanka fa na gaisheta ta yaya kake ganin za mu zauna lafiya da juna bayan duk abinda ta yi daidai ne a wajenka baka nuna mata kuskuranta."
Ya d'aga mata hannu yana cewa." Ya isa ban ce ki gaya mini magana ba, duba da kyau akwai yara ba ni son rashin hankali."
Ta yi shiru ba ta sake cewa komai ba.
Ya yi 'kwafa kafin ya cigaba da ce wa." Kin had'e fuskarki tamau! kina amsa gaisuwa da k'yar a matsayinki na wadda aka zo gidanki hakan shine daidai ko kina tunanin ban ga irin wulakancin da ki ka yi wa yaron nan Adamu ba."
Ta dai yi shiru ba ta tanka ba.
Na daure zuciyata ina fad'in." Hauwa aka ce shimfidar fuska tafi ta tabarma tunda na zauna ban ga kin yi mini duban mutunci ba to me zai sanya ni shiga sabgarki, magana akan katse mini waya kin san dai babu yaro a cikinmu ko, menene amfanin abinda ki ka yi, ko ni ina hana shi amsa wayarki ne?"
Ya daga mini hannu yana fad'in." Na ce ya isa haka ko, kada wadda na sake jin ta yi magana."
Ban sake cewa komai ba naja bakina na yi shiru itama ta yi shiru cikin kunyar abinda ta aikata tunda ta fahimci ni dashi duka mun gane ita ta katse mini waya..

Na yun'kura na tashi ina fad'in." Za mu tafi Baba Allah Ya kara sau'ki." Yaran suka tashi gabad'aya Khalil ya d'auki Sultan suka yi gaba k'ananun kuma suka tsaya ni har muka gama sallama da shi, na dube ta babu yabo babu fallasa na ce." Allah Ya ba mu alheri Hauwa."
Ta amsa kanta a kasa domin ta kasa yarda ta dago ta kalle ni.
Biyo bayanmu ya yi wai sai ya rakamu gida muka kuwa jero muna tafiya tare har bakin gate din gidana har da shi muka shiga ciki ya tsaya yana magana

da masu gadi. Amma bai biyo mu ciki ba anan dai muka bar shi muka shige ciki ni da yaran gabad'aya.
Washe gari kuwa gari yana yin haske na kira shi bugun farko ya daga na ji muryarsa ta fara bud'ewa ba kamar jiya ba muka gaisa yana gaya mini ya warware tarin ma da yake yi ya sassauta masa sosai.
Ita ya ba ni wai mu gaisa duk a kokarinsa na ganin lallai sai mun samu daidaito ban yi jayayya ba na ce to na ji maganarta a dan sake tana fad'in." Ina kwana ya yaran?"
Na amsa da lafiya lou muke  suna can suna shirin makaranta." Ta furta." Allah Ya yi musu albarka."
Na amsa da Amin  a tak'aice."
Daga haka ba ta sake cewa komai ba ta bashi  wayarsa. Muka dan yi magana kad'an ya kashe tunda a ranar zai dawo gidana.

****
Sati biyu  da faruwar hakan. Kawai na ga kiranta na yi mamaki sosai yaushe rabon da mu yi waya ta arziki da Hauwa tun lokacin da ta ajiye Sultan ta tafi garinsu. Haka kawai sai na tsinci kaina cikin fad'uwar gaba domin kuwa zahiri zuciyata ta kasa aminta da ita tun bayan abubuwan da suka shud'e ba ni tunanin zan sake sakin jikina da ita tunda ta gama fito da aninhin abinda yake cikin ranta game da ni.
Na daga cike da tarin zullumi muka gaisa ta yi shiru ba ta ce komai ba na ce." Ina fatan lafiya ko Khalil din za a turo miki ne?." Da yake wasu lukutan takan turo mai yi mata wanki da guga  ya kira Khalil ban san sai dalilin da ya sanya take kiransa ba wannan tsakanin d'a da mahaifi ne shima yaron yanzu yana sakewa da ita ba kamar da ba.
Ta sauke ajiyar zuciya kafin ta ce." Amina tun ranar da ku ka zo duba maigidan hankalina ya kasa kwanciya ganin Nabila ba ki tunanin akwai wata dangantaka ta soyayya a tsakaninsu kuwa? ko ba ki ji lokacin da yake tambayarta ta dawo ba, hakan na nufin suna da wata ala'ka tunda har yana da masaniyar shige da ficen da take yi kan harkokinta."
Na yi kasa'ke da waya a kunne ina sauraranta har ta kammala maganarta. Zuciyata kwata-kwata bata ta'ba yi mini wannan tunanin ba a ganina shi kuwa me zai yi da Nabila duk nagartattun matan da suke wannan duniya. Kai gaskiya ba na tunanin zai yi soyayya da ita ko ya yi zawarcinta.
Ta ce." Kin yi shiru ba ki ce komai ba, kin ga dacewar ko aure zai kara ya yi da ita. Bayan bada'kalar da ta faru da yayarta."
Na furta." Ki daina wannan maganar don Allah Hauwa, ba ni tunanin haka gaskiya Nabila dai kamar yadda ya gaya mini tana zaune ne domin ta zama garkuwa ga yaran 'yar uwarta, cikinsu babu wanda ya ta'ba kawo korafi a kanta hakan ya nuna suna buk'atar zamanta a tare da su. Maganar kuma mijinki yana zawarcinta ai shi ba mahaukaci ba ne a zahiri da suffa Nabila ba macen da ta kamace shi bace balle ga abubuwan da suka faru a baya. Dole za su gaisa watarana kuma suna da lambar juna hakan kuma ba zai sanya mu ce soyayya suke yi ba."

Ta ce." Jikina ne yake ba ni akwai matsala Amina wallahi ko shi baya sonta to ita tana zawarcinsa ai akace idan kaga kare yana shanshana takalmi d'auka zai yi. Sun gaji asiri fa wallahi kada ta juyar masa da tunani mu rasa gane kansa kamar yadda 'yar uwarta ta yi.''
Na ce." Ki daina tunanin haka don Allah." Abinda na iya ce mata kenan domin ni lokacin ma wani matsanancin ciwon kwankwanso ne ya ri'ke ni.
Na ja kafafu na zauna gefan gado ina jin ta sama-sama a haka muka yi sallama. Tunda na ji ciwon ya tsananta sosai na tabbatar da cewa haihuwa ce. Wannan karon kuma abin ya canza mini kenan ba ni haihuwa tara sai na goma ya kama amma watannan kwanansa goma sha bakwai Allah Ya kawo mini ita.
Na tashi na fito da duk abinda ya kamata mussaman kayan baby ina da su akwati guda manyan set na kayan sanyi da towels Na kira
Dr Sailuba  lokacin da sauran k'warina bayan ita ko shi ban gayawa ba balle masu aikin yara kuma duka suna skull minti talatin ta iso lokacin ciwon ya sake k'arfi da kayan aikinta ta taho ta gyara wajen tare da shimfid'a mini wata leda babba ta yi mini shimfid'a a kai na kwanta ta duba ni. Da saura haka na cigaba da fafatawa sai da na k'ara minti talatin da zuwanta tukkuna Allah Ya kawo ta da gaggawa babu jinkiri na farkon
yana fitowa d'an uwansa ya biyo shi jim kad'an mahaifarsu ta biyo baya. Ina kiran sunan Allah itama tana yi bakinta ya k'i rufuwa. Da yake gwanace ta yi komai cikin k'warewa kowanne ta nad'e shi cikin towol fadi take kin iya haihuwa wallahi dubi yara 'kosassu na jima ban ga biyu masu wannan girman ba alhamdulillahi."
Ta shiga toilet dina ta had'a mini ruwan d'umi lokacin na tashi da kaina don ba ni jin komai na canza zani na sanya audiga na kuma tafi da wata toilet din.
Ina fitowa na tarar ta tattare kayan dana haihu a kai babu abinda ya 'baci a d'akin kamar ma ba a yi wata sabga ta jini ba.
Na fito da kayana da kaina na sanya da kanta ta wanke yaran suna ta kusur-kusur kuka wannan idan ya dire sai wannan ya d'auka. Muka fara jin bugu muryar Baba Tabawa tana kiran sunana. Hajiya Amina. Taburni tana fad'in." Haihuwa ta yi wallahi tallahi ga kukan jariri nan.
Na tashi ina murmushi a nutse na je na bud'e musu d'akin suka shigo gabad'aya su uku har da Mairo.
Dr dai sai dariya take yi musu tana aikinta. Baba Tabawa fadi take yi." Ba ku kyauta mana ba amma."
Gabad'aya bakinsu ya'ki rufuwa.  Mairo tana dariya take ce wa." Shikkenan biyu sun samu 'yan uwa Allah mun gode maka, Ubangiji Allah Ya yara mana."
Taburni ta d'an zauna gefena tana fad'in." Sannu Ubangiji Allah Ya kara lafiya Hajiya Allah Ya hore miki arziki domin wannan baiwa ce daga wurin Ubangiji Allah Ya inganta lafiya."
Na amsa da Amin suma Amin."
Baba Tabawa ta kwashi kayan da suka 'baci ta fita da su. Ta burni ta bi bayanta da sauri.

Ita kuma Mairo muna tare tana zubar da ruwan wankan yaran tare da had'a wani a haka Dr Sailuba ta shiryasu tsaf cikin kayan sanyi kowane da towel dinsa abin dai gwanin burgewa, ni kam tunda na zauna gefan gado nake tasbihi tare da jaddada godiyata ga Allah ganin yadda ya yi mini wannan baiwa ta haihuwa lafiya ba ni jin komai a jikina ina kuma addu'a a gare shi ya sanya ko da an auna yaran a tabbatar mana da sahihancin lafiyarsu.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*160*
Wannan haihuwa ta yi silar wanke zuk'atan bayin Allah da yawa. Tun daga kan masu gadin gidansa da yaransa na jiki irinsu Sukairaju da masu hidima da kai kawo na gidan muka kasance gabad'aya da su cikin
murna tamkar a daran sallah. Ita dai Dr Sailuba ta samu tukwicin kujarar umara da mota. Masu aikin kuwa Baba Tabawa Mairo Taburni kowacce da alk'awarin zuwa umara ta azimi kuma tunda daf muke da shiga watan. Ya rasa inda zai sanya ransa ya ji dad'i da ya dawo ya same ni da yaran lafiya lau kuma Dr Sailuba tana gaya masa cewa ita dai a yadda take ganin yanayin kuzarin yaran bata tsammanin suna d'auke da wani ciwo mai karya garkuwar jiki mussaman irin wanda muke hasashe amma domin dai a sake tabbatar da lafiyarsu lau ya ce mata za mu je asibitinsu tare da ni dashi wajan Dr Iliyas a bincikesu sosai don mu sake samun nutsuwa da kwanciyar hankali.
Sujudur Shakur ya yi a gabana ya jima kuwa goshinsa a kasa da ya d'ago sai ya kama ni
ya rungume ni tsam-tsam a jikinsa yana ta furta mini kalmar godiya tare da jadadda mini so da k'aunar da bata da abin misali.

Yara suka dawo daga makaranta tsalle suke yi Mama ta haihu abinda suke ta fad'i kenan sun kewayemu da Babansu. Ya ce su je su cire uniform suka 'ki lallai sai an ba su sun d'auka.
Kowacce ta tan'kwashe k'afa ya dinga bin su d'aya bayan d'aya yana dora musu a cinya. Usaina sai dariya take yi tana kallonsa ta ce." Baba ka ga hancin wannan irin nawa ko? dama Mairo ta ce da ni suke kama?''
Hassana kamar wata shashasha ta ce." Ni zan dinga goya d'aya kema ki goya daya ko?"
Minal ta ta'be fuska za ta yi kuka tana ce wa." Baba ni fa? ni ma ina nawa wanda zan goya."
Sai kuka hawaye share-share suka shiga kasa tsare a kumatunta. Ya janyota da saurin gaske ya d'ora saman cinyarsa yana share mata hawaye. Ta rike

shi tana kuka tana fad'in." Ina nawa yake Baba." Na kar'bi Usainin daga hannun Hassana na ce." Ga naki nan shine Usaini na bar miki."

Ta fara ko'karin ri'ke shi nasa mata a jikinta ya tare da hannunsa. Ta saki dariya tana ta'ba kumatunsa ya d'an bud'e ido d'aya sai kuma ya rufe tasa dariya tana cewa." Baba ka ga ya bud'e idonsa nan d'insa ya yi ja ko ciwo ya ji." Ta nuna kumatunsa da wani tabo a wurin wanda ya yi jaa sosai ya bambamta da fatarsa. Da wannan alamar Allah Ya bambamta mana su Amma kamanninsu daya shi Usainin ne mai wannan tabon.

Ya ce." Ba ciwo ya ji ba haka Allah ya yi masa baiwa."

Ta ce." Mama kin bar mini shi ko?" Na d'aga kaina. Yarinyar bakinta ya'ki rufuwa tasa yatsanta a cikin hannunsa ya kuwa d'amke ta dinga k'yalkyala dariya tana duban 'yan uwan "kin gani ko ya rike ni, Usaina kin ga ya rike mini hannu."

Su dai dariya kawai suke yi mata. Khalil ya shigo bakinsa har kunne da yake sun riga shi dawowa shi yana cikin yaran da za su yi saukar al'kur'ani sun bambamta musu lokacin tashi mahukunta makarantar.

A nutse na ce." Shigo sosai mana." Ya shigo yana ta washe baki ya ce." Masa'udu ne  ya gaya mini Mama ta haihu kuma guda biyu Irina."

Uban ya kama yi masa dariya. Ya matsa kusa da shi yana ta duba fuskar yaran ya kar'bi na hannun Usaina yana cewa." Wannan shine a babban mama." Na ce." Shine na hannun Minal kuma Usaini." Abinda ya yi gabad'aya sai da ya ba mu mamaki har uban ya rungume shi a kirjinsa ya rintse idonsa kimanin minti biyu ya bud'e cike da kwalla ya dinga fad'in." Allah Ya raya ku, Allah Ya sa mu yi zumunci domin Allah mu so junanmu domin Allah, Ubangiji Allah Ya yi wa Babanmu tsayin rai."

Na yi saurin sunkuyar da kaina kasa jin k'walla ta cika mini ido. Yaron nan yana da kaifin basira da tunani. Yasan shekarun girma sun cimma Babansu gasu k'ananu shine yake wannan addu'ar yana so su girma tare dashi

Shi kansa jikinsa sai da ya mutu. Amma da yake namiji ne bai nuna rauninsa ba yaron ma yana addu'a amsa masa yake yi. Sai da ya gama tukkuna ya ce." Za mu je umara bayan mun yi bikin suna ni da kai ko Babana." Ya gyad'a kansa cikin dauriya da ko'karin hana 'kwallar idonsa zuba." Ya furta." Akwai wurin da zan nuna maka jikin d'akin Allah sai ka tsaya sosai ka roke Allah Ubangiji Ya raya ni cikinku na ga girmanku ko?"

Shiru ya yi bai ce komai ba 'kwallar dai da yake ko'karin hana ta zuba ita ta fara d'igowa saman towel din jaririn da yake hannunsa.

Ya ce." Menene haka kuma Baban masu gida, a gaban 'kananka za su yi maka dariya."

Ya d'an share hawayen ya fakaice ya dube ni yana cewa." Mama."

Na amsa Ina kallonsa da wani irin yanayi gabad'aya duk ya dakusar mana da walwalarmu."

Ya cigaba da cewa." Mama ta ji kin haihu ko na je na gaya mata?"

Na ce." A a bata ji ba dama jira nake ku dawo daga makaranta."

Ya tashi tsaye da yaron a hannunsa Usaina na mik'a hannu ya bata ya k'i ya mi'ko mini uana fad'in." Zan je yanzu na gaya mata."

Na kar'be shi a hankali na ce." To hakan ya yi."

Fita ya yi daga d'akin da d'an sauri.
Muka dubi juna ni da shi bai ce komai ba haka zalika ni ma haka. Na dube su a nutse na ce. "Ku je ku cire kayan makaranta a yi alwalar magriba sannan a samu nutsuwa a ci abinci."
Suka tashi a tare har ita Minal din da take saman cinyarsa ya kar'bi yaron dama kusan rabi a hannunsa yake ta dira kasa tana kallona ." Mama za ki goya mini shi idan an jima ko?"
Na gyad'a kaina alamar E ta juya da niyyar fita tana d'an tsalle.
Shiru na wani lokaci kafin na ji sautin numfashinsa." Ko yanzu Ubangiji Allah Ya d'auki raina Amina kin gama biyana hakika alherin da yake tattare da tarayyata dake ba zan k'idaya shi babu abu mafi girma da arziki face wannan. Allah Ya saka da alheri, ba zan boye miki ba na jima ban tsinci kaina cikin yanayi na farinciki kamar wannan rana ba. Sai dai jikina ya yi sanyi ainun da lamarin yaron nan Khalil ko lokacina ya kusa ne zan tafi na bar ku."
Hararsa na yi ina fad'in." Kai ma abinda za ka yi kenan wace irin magana ce wannan don Allah."
Ya dubi fuskar yaron da yake hannunsa a tsanake ya ce." Sai dai shekarun girma suka cimmani Ubangiji Allah Ya azurta ni da 'yan baiwa gasu nan kin san dai ba zan maimaita shekarun da na yi a baya ba ko Annabi Muhammadu s a w ya ce sittuna au saba'una. Yanzu hamsin da takwas nake."
Shiru na yi ban ce masa komai saboda takaici mutuwa dole ce amma a ganina bai kamata a kawota a yanzu da muke cikin annashuwa ba.

Wannan littafin na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Wayarsa aka kira ya canza harshe larabci yake yi sosai. Na tsinci wasu daga cikin abinda yake fad'a wasu kuma ban fahimta ba yana dai ta fad'in sunan Sukairaju a maganarsa ya gama ya dube ni yana fadin." Ba'ki na yi daga madina akan wani lamari ina barar addu'a."
Na ce." A cikinta nake kullum Allah Ya yi riko da hannayenka, ni ma na gode sosai Allah Ya saka da alheri."
Ya tsare ni da ido yana fad'in." Me na yi na godiya Amina?"
A takaice na ce." Abubuwa da yawa. " Ya yi shiru bai ce komai yana dai ta kallona ina kici-kicin gyara rigata ya taimaka mini Hasan din ne yake mamulan baki da neman abinci ya d'ora mini shi saman cinyata na tallafe shi sosai nasa masa nonon a baki. Ya kuwa kama  yana sha yaran yanzu duka da wayonsu ake haifarsu amma dai duk da haka na d'an taimaka masa wajan ganin ya rike a bakinsa.
Ya ce." Idan Allah Ya kaimu za mu je asibiti tare kamar yadda na fadi da farko domin a duba mini su."
Na ce." Allah Ya kaimu." Ya duba agogon dake d'aure a hannunsa magriba ta yi ya shiga toilet dina ya dauro alwala ya fita zuwa massalaci.
Duka su biyun na shayar. Baba Tabawa ta shigo tana fad'in.'' ko akwai abinda nake buk'ata wanda zan ci. Na ce ta dama mini kunun gyada kawai na fara

dumama cikina an jima idan na yanke shawara akan abinda zan ci zan gaya mata.
Ta dubi yaran suna kwance a gado bacci suke yi ta furta." Ko za a goya su ne Hajiya?"
Na yi dariya tare da fad'in." Sultan din fa?"
Itama tana dariya ta ce." Ai ya girma shi ya zama saurayi."
Na ce." Mu bari zuwa gobe tukkuna Babansu zai dawo."
Ta gyadq kai tare da juyawa da sauri ta fita.

Cikin kwanaki biyu da haihuwa dangina da nasa babu wanda bai ji ba. A kuma yau da suke da kwanaki uku a duniya Hajja da yayarsa Hajiya Saratu suka sauka a garin da abin arzikinsu akwati biyu cike da kayan yara kowanne da tasa
Anti Yagana kuma ta ce mini itama dai tana tafe da muka yi waya da ita. Baban Saude kuwa kwana d'aya da haihuwar ya zo bakinsa kamar zai yage ganina kalau yaran ma haka domin ni da shi baban nasu mun sake samun nutsuwa da kwanciyar hankali a lokacin da aka tabbatar mana da ingancin lafiyarsu sai farinkinmu ya sake hauhawa. Kwana ya yi da safe bayan ya karya kummalo ya yi mana sallama ya wuce wajan sana'arsa har yana yi mini alkawarin zuwan iyalinsa tunda mun ce da taron suna ko dai ba su zo gabad'aya ba Anti Saude da Mamansu za su zo idan mun tsayar da ranar da za mu yi bikin sunan ya ce na gaya masa.
Na yi ta murna kuwa ina yi masa godiya kafin ya tafi.
Shud'ewar wannan kwanakin babu Hauwa babu dalilinta. Khalil ya gaya mata ranar dana haihu haka zalika ma mijinta ya gaya mata da bakinsa ya gaya mini ta sani. A yadda na fahimta yana tunanin ta zo tunda ba yini yake yi a gida ba tunda ya yi ba'kin nan bai zauna ba sai da daddare yake shigowa kuma kwana daya da haihuwar ta kar'bi girki. Yau da su Hajja su ka zo ya dawo gidana.
Zuwa yanzu ni ma na fito falo cikinsu amma ta ko'ina jikina a rufe yake kafafuna ma koyaushe suna cikin safa. Tunda na haihu Allah ya hore mini lafiya ba ni jin ciwon irin na gigita bayan haihuwa kuma babu abinda ba na gudanarwa na abinda ya shafe ni. Wannan kad'ai ya isa na godewa Ubangiji.
Rashin zuwan Hauwa ya ta'ba mini rai ainun na kuma yi mamaki ba kad'an ba.
Masu aiki na hidima da yara ta kowace siga kowa k'auna da kulawa yake nuna mini me zan ce da Ubangiji. Salim baya garin yana Legos amma Nusaiba zuwanta biyu Adam ma tunda na haihu yake shigowa haka zalika ma Nabila ta shigo mini kwana daya da haihuwa ta yi mini barka sosai ta fita...
Kwanansu Hajja biyu ranar biyar kenan suka fahimci akwai matsala daga bangaran Hauwa dalili da ni da maigidan da masu yi masa hidima daga waje har zuwa cikin gidan kowa cikin annashuwa yake yi. Hakan ya ta'ba ran Hajja sosai ina d'aki ta same ni, ganin yanayinta ya sanya na nutsu ta zauna a gefena tana duba fuskar Usaini ta ce." Wannan tabon kamar sake rinuwa yake yi a fuskarsa Amina."

Na ce." Ni ma na lura da hakan, amma dai Dr Iliyas ya ce babu matsala in sha Allahu."
Ta sauke ajiyar zuciya a hankali kafin ta dube ni ta ce.'' Menene a tsakaninku da Hauwa, Amina kada ki b'oye mini komai wannan lamarin naku ya fara damuna ya kamata a ce kun girma tunda duka babu yaro a cikinku."
A hankali na furta." Babu komai sai alheri Hajja ranar da zan haihu ma mun yi wa da ita a sanina dai babu wata hatsaniya da ta ratsa tsakaninmu."
Ta yi shiru na d'an wani lokaci kafin ta ce." Ki gaya mini gaskiya ta shigo gidan nan tunda ki ka haihu?"
Na girgiza kaina ina fad'in." Ba ta shigo ba."
Ta furta." Ki ce kuma babu komai Amina haihuwa irin wannan akwai dai wani abu da kuke b'oye mini?'
Na ce." Hajja babu komai wallahi ni dai a nawa b'angaran ban san nata b'angaran ba."
Ta ce." Ke ai na yarda dake Amina kuma na gazgataki domin da da akwai matsala za ki gaya mini, Hauwa ba ta jin maganar kowa, ta raina ni ta raina uwarta kuma ba ta jin shawara."
Na yi shiru ban ce komai ba.
Ta girgiza kanta da damuwa a tare da ita ta tashi ta fita. Sai ta d'an ba ni tausayi domin na gane duk fafutukar da take yi akan gidan d'anta ya gyaru da kamar wuya wai gurguwa da auran nesa Hauwa ta bari hassada ta yi mata illah a rayuwarta.
Da daddare muka yi waya da anti Yagana cewa suna tafe ita da Ya Falmata ta dawo sati biyu da suka wuce. Na yi musu addu'ar isowa lafiya.
A daran dai da ya dawo wajan goma da wani abin ban jima da yin sallama da su Hajja ba na shiga d'aki domin gasa jikina na kwanta na fito daga toilet na same shi rungume da Hassan yana kafadarsa  ya tashi daga bacci yaran suna da tsotso mussaman da daddare Usainin na goye a bayan Taburni yana bacci.
Na sanya kayan bacci a gurguje na kar'be shi domin kuka yake yi sosai na zauna nasa masa nono ya kama. D'akin ya d'auki shiru na wani lokacin kafin ya ce." Gobe ba'kin nan da na yi za su tafi amma jin labarin k'aruwar dana samu suka ce za su zo yi miki barka wasu labarawan Madina ne sharifai ne jinin Annabi Muhammadu S.a.w suka  ce wai na tambaye ki za ki ba su yaran?"
Na dube shi cikin rashin gane inda maganarsa ta dosa na basu  yara kamar Yaya?"
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Sun ji irin jikokin Annabi Muhammadu S.a.W ki ke haifa kin san akwai su da kara da karamci da tsantsar ha'din kai
sun ta ya ni murna sosai da abin alheri suka ce a baki."
Dariya na yi na ce." Aikuwa na gode sosai amma dai su yi hakuri ba zan ba su ba."
Yana dariyar shima ya furta." Kai tsaye abinda na gaya musu kenan, sun ce wai ke y'ar baiwa ce ta mussaman kina haihuwar yara masu daraja da albarka."
Murmushi kawai na yi

Ya nisa kafin ya cigaba da cewa akwai kud'i da na bawa Nabila za ta had'o musu kaya akwati hud'u Hasan biyu Usaini biyu idan kin duba abinda bai yi ba ko ake buk'ata sai ki yi magana ko?"
Na dube shi sosai ina fadin." Akan me za ka bata kudi kace ta had'o mini kaya, me yasa ba ka yi shawara da ni ba ko ni ban  san abinda ya dace da su ba?"
Ya ce." Hajiya sassauta mana ita ta nema ba ni naga dacewar bata kudi ta sayowa yarana kaya ba business d'in ta ne da take yi kenan da aje waje a sayo sai a saya a wajenta ko?''
Shiru na yi ban ce komai ba. Ba zan yarda da wannan shishshigi ba duk abinda yake tsakaninsu ba ni buk'atar ji, jiki magayi ne duk tsuntsun da ya ja ruwa shi ruwan kan doka. Ba ha'ka mai ya kawo rami, idan ta yi wari sai mu ji ai!
Ya cigaba da cewa." 'Kiyasin kud'in nan da mutanan nan suka ba ki a matsayin alheri na haihuwar yaran nan sun haura miliyan saba'in. Ni kuma na ba ki tukwucin 'karamin kamfanina na soap (sarrafa sabulun wanka) wanda yake mariri."
Da wani irin mamaki na dago ina kallonsa miliyan saba'in!
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Kad'an kenan daga irin alherinsu ba wani abu ba ne, kin cancanci fiye da haka Allah Ya yi miki albarka."
Na ce." Me yasa za ka ba ni kamfani guda?''
Kai tsaye ya furta." Saboda ina shirye-shiryen bud'e wani zuwan da suka yi kenan!''
Na girgiza kaina a hankali na ce." A a ba zan kar'ba ba gaskiya ka haihu fa, nan gaba da ni da kai ba mu san iya adadin yaran da za ka sake haifa ba duk neman da za ka yi a yanzu saboda su za ka yi don haka ka bar shi na gode sosai da kulawa da addu'a abinda ka yi wa yarana wad'anda ba kai ka
 haife su ba wallahi ya ishe ni."
Ya furta." Wanne yara ne ban haifa?'' Ya tsira mini ido da jin haushin maganata.
Na cire idona daga cikin nasa a hankali na kwantar da yaron ina fad'in." Ni dai ba ni neman fitina don Allah idan alheri ka yi niyyar yi mini ka yi daidai gwargwado wannan ya yi yawa.''
Ya ce." Abinda na yi niyyar bayarwa kenan Amina."
Na yi shiru ban ce komai ba amma zuciyata cike take da mamaki bayan zunzurutun kudi har miliyan saba'in da kamfani guda abin kamar ya yi yawa fa.
Koda su anti Yagana suka zo na gaya musu Ya Falmata ta dinga fad'in bake ki ka ro'ka ba baki ya yi akan me za ki ce masa ba kya so. Kowace haihuwa da alherinta tunda har ya iya mallaka miki kamfani to dukiyarsa takai ta kawo wata'kila shima bai san adadinta ba, idan kin lura bayarwa yake yi tana sake ru'banya. Allah Ya kawo wasu abokan nasa su sake baki arzikinki ya ninka na da mu abinda muke so kenan.
Ita dai anti Yagana shiru ta yi da alama yadda abin ya girgiza ni haka ya girgizata. Ta kasa cewa komai sai kallo.

Zuwansu anti Yagana ya 'karawa gidan walwala domin dama can akwai jituwa tsakanin Hajja da ita gefe guda kuma ga Ya Falmata sarkin barkwanci da bada dariya ta zauna tana ta ba su labarin matan da suke zaman shahada a makka da yadda suke shan tiriri da wahala guje-guje itama abinda ya koro ta kenan.
A daran ranar duka muna falon an gama cin abinci sai ga Hauwa ta yi sallama ta shigo Khalil na biye da ita a baya.......✍
*GARKUWAR BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*161*
Ni tausayi ma ta ba ni ganin gabad'ayanta kamar a ki'dime take da wannan yanayin na rashin gaskiya da kame-kame duk a k'okarinta na kare a kanta suka gaisa da Hajja tana ta nanata musu cewa ba ta da lafiya a kwance take har yanzu jikinta babu dadi har da 'yar 'kwallarta wai an gaya mata kwanansu biyu da zuwa amma ba su je gidanta ba.
Hajja dai shiru ta yi mata kawai ta zuba mata ido Hajiya Saratu ce ta tanka mata itama ba wata magana mai tsayi da muhimmaci ba. Yadda dai ta girba 'karya tare da d'orawa kanta ciwo duk mai hankali yasan da cewa k'arya ce tsagwaronta babu wani mashahurin ciwo a tattare da ita balle ya hana ta zuwa duba jininin d'an uwanta. Ko ba ta zo domin ni ba tunda kishiyarta ce ta zo domin mijinta kuma d'an uwanta balle ma ni ban ga abinda na yi mata mai muni ba da zata sanyawa ranta k'iyayyata mai zafi. Haka kowa ya bi ta da abinda take fad'i ana ta yi mata sannu da jiki
tana rantsewa da Allah wai bata da lafiya itama. Ni kuwa na tabbatar da cewa k'arya take yi tunda halinta ne d'orawa kai ciwo haka take yi ko kunya ba ta ji. Da haka muka gaisa da ita suka gaisa da su anti Yagana babu wanda ya nuna mata wani abu a fuska Ya Falmata ma sai tsokanarta take wai ko itama ta ci wake ne. Ganin haka ya sanya ta saki jikinta saboda yadda aka goya mata baya cewar bata da lafiya har su Hajjan gabad'aya. Khalil ya dinga jin dadi yaron ya d'auki yaran d'aya bayan d'aya ya kai mata tana duba su tana dariya wadda nasan ba ta jin dadi ba ce fadi take kamarsu daya da Babansu yadda ake ta fad'a haka take cewa har tana kallona mun fi ki karfin jini Amina.
Ban iya ce mata komai ba sai kallo kawai domin koyaushe sabon darasi nake d'auka daga gareta. Ana haka maigidan ya sakko ya kuwa ji dad'i ganinmu tare da ita gabad'aya ana wasa da dariya shima ya zauna duk da akwai rashin sakewa tsakaninsa da su anti Yagana mussaman Ya Falmata kunyarta yake ji tunda yasan 'kanwar Mamana ce, bai dai za'ke sosai ba ana hira da shi jefi-jefi hankalinsa ma yafi karkarata kan yaransa da zamansa a wajan ya sanya suka kewayeshi. Ita kuwa Ya Falmata bata suruktaka da shi ta cigaba da sakin bakinta daidai misali a yi dariya idan ta kama a kuma jajanta a cikin abinda aka tattauna.

Tare suka tafi tunda dama kwanaki d'aya kenan da kar'barta girki gobe ne zai dawo gidana ya kwana.

Washe gari da wuri yarinyar nan Lad'ifa ta zo ta zauna zaman yi mana 'kunshi ta fara yi mini jaa kimanin awa biyu aka cire ta zana mini fulawa ba'ki a kafafu da hannu. Ya Falmatace za ta yi mini kitso idan sun cire lallan da aka yi musu domin ita da anti Yagana sun ce suma ba za a bar su a baya ba.
Wajan biyar na yamma sai ga tawagar gidanmu Gwaggo ce kawai babu domin bata jin dadin shine dalilin da ya sanya ba ta samu zuwa ba tabbas da nasan tare za su taho da su Hajja.
Mamaki ya kama ni sosai mota suka biyo ta haya hakan kuwa bai yi mini dadi ba tunda da sun kira ni sun gaya mini nasan idan na gaya masa zai iya sanya direba ma daga can ya d'aukosu duk yawansa.
Sahura da Yusura da yaronta da ba su jima da yin arba'in ba. Ummansu Hadiza da Ummansu Saminu Fati da Hassana da Usainar gidanmu sai matar Hamusu itama amma ba ta zo da yaran ba suna can wurin Gwaggo Yusi shine jagora. Da kuma Ummatu babarsu Sunusi uwargidan Baba Sule kuma k'anwar Ummansu Hadiza ce ubansu d'aya. Sai Fiddausi yarinyar da ta zauna a hannuna lokacin bud'e gidana na kuntau ita da Yusura a lokacin da na ta fi umara ta farko kaddarar aure ta ratsa tsakani muka rabu ta koma gidansu. Duk ga su yau dalili ya kawo mini su.
Ita kuma amarya Hajara matar Usaini ana can babu lafiya yadda Fati take gaya mini suna zargin ciki ne da ita ciwo take yi sosai har da su k'arin ruwa. Ikon Allah kenan
Wannan zugar da suka yi ta tabbatar mini da cewa dama sun shirya sun kuma tsara yadda tafiya za ta kasance amma rashin gaya mini shine abinda ya b'ata mini rai.
Sashenmu na ba'ki dake gidan na sanya aka gyara musu 'yan gidanmu kenan suka yada zango a can su Baba Tabawa na ta hidima da abinda za su ci. Sahura da Yusura kuma muna tare da su. Ita kadai ce na san da zuwanta a yau din saboda kayana da za ta kawo mini tunda mun yi waya da Hamusu ya ce mini ya kai mata tun kwana biyu da suka wuce amma shima bai gaya mini matarsa na tafe ba.
Sun yi mini bazata kuma na ji dad'i masu k'orafin ba su ta'ba zuwa ba dalili ya kawo su. Amma har yanzu ni dashi ba mu tsayar da ranar walimar ba. Kwana shida da haihuwa a yau din kenan gobe yara za su sake amsa sunansu amma ba ni tsammanin a ranar za mu yi taron walima kamar yadda ya saba duk haihuwar da za a yi masa alamu sun nuna akwai shirye shiryen da yake yi.
A daran da ya shigo na bi shi saman duk da ba girkina ba ne na Hauwa ne amma wasu lukutan yakan shigo ya yi sabgoginsa kafin ya fita kamar yadda idan ya je can yake yi, kuma ban ta'ba kalubantarsa ba ganin yadda shima yake takatsantsan da gujewa abinda zai kawo masa rikici yana wanka na zauna ya fito da ya gan ni a zaune sai ya d'auke kansa ya tafi ya tsaya gaban mudubi kad'an ya shafa basiline a jikinsa ya fesa turare ya sanya kayan shan iska fuskarsa ta nuna mini akwai abinda yake ji wa haushi.

Gaishe shi na yi ya amsa tare da zama gefena na d'an tsura masa ido ina kallonsa shima yana kallona kafin na ji ya furta." Zan ga ranar da zan yi miki abu ki yaba mini Amina har yanzu ban iya ba a wurinki na gode k'warai kin kyauta."
Na ce." Wani abu ne ya faru kuma?"  Da wani irin yanayi ya ce." Saboda na baki wani abu da bai kai ya kawo ba shine ki ke bin 'yan uwanki kina gaya musu menene abin magana akan abinda na yi anan a gaya mini hujjar da ta rahamta mini yin kyauta da  abinda nake so da dukiyata. Ke na ce na bawa wannan wuri ba 'ya'yan da muka haifa tare ba. Ko na ta'ba yi miki wata babbar kyauta duk tsayin zamana dake bayan wannan?"
A d'an sanyaye na ce." Wa na gayawa ka ba ni kyauta?"
Don har ga Allah ban yi tunanin su anti Yagana za su yi masa wata magana ba tunda ni su kadai na gayawa Babanmu bai sani ba haka zalika ban sanar da Baban Saude ba.
Ya gyad'a kansa yana fad'in." D'azu da safe kafin na fita 'yar uwarki ta same ni a haraba tana yi mini wasu maganganu shin me kuka d'auke ni ne? jahili wanda ba shi da ilimin addini ko me? kyauta ke na bawa ba yara ba. Ko kuwa idan na yi Hauwa ko a ahalinta alheri sai kowa ya sani. Za ku nuna mini yadda zan yi da abina ne Amina. Duk abinda nake yi ina sane babu wani yaro da zan haifa walau ke ki ka haifa ko ba ke ki ka haifa ba na fifita shi akan d'an uwansa. Ko an ce dole idan na kwanta dake a daren girkinki itama sai na kwanta da ita. An tilasta mini cewa idan na yi jima'i da Hauwa yau gobe sai na yi da Amina?."
Shiru kawai na yi ina kallonsa da mamaki. Lallai anti Yagana ashe shiyasa ta yi shiru bata tanka mana ba ashe da akwai abinda ta kud'irta a ranta yadda dai ransa ya 'baci hakan ya tabbatar mini da cewa ta fad'i maganar da ta tunzura shi kamar yadda yake nanata cewa dukiyarsa ce kuma duk abinda yake yi yana sane shi ba jahili ba ne.
Ya cigaba da cewa."
Babu d'ayanku da nake da ta'kidin takewa ha'kki ko na fifita yaranta duka ni na haifa kuma babu wanda bana so a cikinsu ina kuma addu'a Allah kada ya kama ni da hak'kinku, hakan kuma baya na nufin na sarayar da iko da mutuncinta ba duk wadda ta yi mini ba daidai ba a cikinku zan yi mata hukunci daidai gwargwadon abinda ta aikata mini. Idan har ba ki son abinda na baki shikkenan kada ki kuskura ki kara wata magana da wani zai tsaya gabana  ya kalubalence ni. Na duba dacewa da cancanta a kanki ne Mutum nawa ne suke 'kasan ki? kuma mutum nawa suke ci da sha a karkashinki? mutum nawa ki ka tallafa suka tashi? ko kuma kin d'auka haka nake zaune dake kara zube ba ni bin abubuwan da ki ke gudanarwa
arziki na Allah ne amma menene makomar yaranki da koyaushe ki ke nanata mini  cewa ba ni ne ubansu ba. Idan yau na fa'di na mutu a shari'a ba su da gadona. Idan na d'auki abu na baki sai ya zama lefi da tiri-tiri da magana kamfanin majizai na baki ne Amina?"

Na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Har yanzu bakina a mace yake na kasa cewa komai saboda mutuwar jiki da mamaki duk yadda yake ganin k'ima da mutuncin anti Yagana yau ta kai shi bango tunda gashi yana ba ni sa'ko zuwa wajenta. Na rasa abin cewa kawai sai na yi shiru da bakina domin ba ni so kuma lamarin ya girmama shi da ita anti Yaganar babu wanda zan za'ba tana da hujja shima yana da tasa hujjar kamfani kuma muddin ana so na kar'ba akashe shi ya daina aiki koma gabad'aya a sayar mini da shi a bani kudin na had'a da wanda suke hannuna alherin da abokansa suka yi mini na nemi plaza cikin kasuwa na saya ko Kuma na sanya k'wararru su gina mini na sake fad'ada harkokina wannan shine magana.
Adamu ne ya kira shi a waya ina ji suka gama magana  yana gaya masa gasu nan shi da Yusi za su kawo sa'ko in ji anti Nabila ita ba ta kira shi ba saboda tasan yana gida sai ta sanya yaran.
ya ajiye wayarsa to a nan ne na magantu cikin had'e rai na ce." Ka ajiye wannan kaya domin kuwa yarana ba za su sanyasu ba Allah shine d'aya ko kuma kawai ku yi tanadi kai da ita idan kun yi aure kun haihu shikkenan kun huta. Ko sun kawo kayan nan a banza, idan lallai sai Nabila ce za ta sayowa yaran nan kayan sanyawa a bar shi kawai zan saya musu a matsayina na uwarsu."
Bai juyo ya dube ni ba ya ce." To shikkenan ai tunda kin ce haka ta riga ta sayo sai a ce mata me? ki a ajiye kada Allah Ya sa ki yi musu amfani da shi din."
Na ce." Ba kuwa zan yi ba, ai ga shawara nan na baka za su yi maka amfani idan kun haihu."
Ya dube ni yana fad'in." Kina da hankali kuwa
Giwa da wa zan haihu?"
Na tare shi da sauri ina ce wa." Da ita mana ko ka d'auka shashashai ne mu, ka ji kunya wallahi."
Ya 'bata ransa yana fad'in." Yanzu ke tsakani da Allah ba ki ji kunyar yi mini wannan maganar ba, duk kalolin matan da suke duniyar nan Amina na rasa wadda zan aura sai wannan matar me zan yi da ita?"
Na ce" Me yasa zan ji kunya tunda kai ba ka ji ba. Haba Malam babu wata magana da za ka fad'i wallahi tallahi na yarda da kai, ina ruwanka da ita da business dinta ka sayi kaya a wajanta saboda kana tausayata mata ko akwai shagunan sayar da kayan baby's cikin garin nan da yawa me yasa ba za ka je da kan ka ka sayo ba, ka bi dare da rana ka samar da cikinsu sayo musu kayan da za su sanya ne zai gagareka."
Ya girgiza kansa yana ce wa." Ba zan shiga shago sayan kaya ba. Ni ma wanda nake sanyawa telana ne yake kawo mini su a dinke ya san irin yaduka da shaddodin da na fi so ko tafiya na yi kin ta'ba ganin na sayo muku abu, idan kina ganin za ki iya zuwa ki sayo musu  abar maganar don Allah don Annabi zan baki kudi wannan din kuma sai a ajiye idan Allah Ya sanya na samu wasu biyun daga wajan Hauwa shikkenan na huta.
Ta'be baki na yi tare da d'auke kaina ban ce komai ba.

D'akin ya d'auki shiru na wani lokaci kafin na ji maganarsa yana fad'in." Kafin na shigo na ga alamar muna da ba'ki tun daga haraba hakene?"
" 'Yan gidanmu ne!" Na fad'a a takaice. Ya saki fuska yana fad'in." Sun zo taya mu murna kenan, na ji dad'i sosai kuma idan na ci abinci zan sakko 'kasa mu gaisa sai a yi musu magana."
"To." Kawai na ce na tashi tsaye. Ya rike hannuna na koma na zauna kusa da shi. B'akin lallen da ya zanu a saman fatar hannayena ya shiga dubawa. Ya bud'e tafikan hannayen yana kallo yatsun ya yi marron sosai zanan fulawar ya fito. Ya dinga sauke ajiyar zuciya yana fad'in." Ya yi kyau sosai mu ga na 'kafafun." Gim na yi kawai ta yaya zan iya nuna masa k'afafuna na cikin safa. Ya sunkuya kuwa ya cire safar yana ta dubawa na zubawa 'keyarsa ido takaici da haushinsa ya ishe ni. Maganar Nabila idan har ta yi nisa akwai wani gagarimin lamari da zai faru tunda shi bashi da tunanin yin nesa da mu'amula mai tsayi da ita bayan gaisuwa. Ai tsakanin mace da namiji idan sha'kuwa da tausayi suka shigo ciki akwai alamun kauna. Ya nuna son cigabanta da tausaya mata tunda idan an yi magana sai ya ce business d'inta ne a saya a wurinta kada a je waje a saya.
Ya d'ago da wani irin yanayi na yi saurin d'auke kaina ya tsira mini ido har yanzu hannunasa yana cikin nawa ya ce." Za ki ba ni abinci ko na tafi na kwanta a haka?"
Na furta." Duk yadda ka ga ni, amma ai ba ni ce mai baka abincin ba."

Ya ce." Kwana biyu itama tana ta ciwo kullum a kwance take ciki ne da ita ba kuma sosai take sarrafuwa ba ke kuma kin ga kina da masu aiki." Na katse shi da gaggawa ina fad'in.'' Na hana ka d'aukar mata aiki ne? tana da lafiya bata da lafiya ba abinda ya shafe ni ba ne. Cikin dai masu aikin gidan nan Wallahi babu wadda za a d'auka.''
Ya ce." Ba a ce dama za a d'auki ko daya ba, za a kawo mata nata masu aiki itama."
Na d'auke kaina ban ce komai ba. Ya ce."
A kawo mini abincin dai ko ba shi da yawa kada abin ya yi mini yawa kuma." Na tashi kawai na tsinci hannunsa saman tudun mazaunaina. Na juyo da sauri ina kallonsa. Ya cire hannun shima yana kallona. Wato da bai samu sararin d'ora hannunsa a kirjina ba kamar yadda ya saba sai Allah Ya bashi sa'a ya d'ora a na baya.
Ya furta." Menene fuskata za ki buge na tare."
Na janye idona daga kansa kawai na wuce cike da mamaki wai tambayata yake yi menene saboda na kalleshi wato shi bai d'auki abinda ya yi a matsayin wani abu ba."
Ina saukowa na tarar da ita ta zo ana ta hira da ita. Usaini ma yana hannunta. Hasan din na goye bayan Taburni yana bacci.
Ta miko mini shi tana fad'in." Tun d'azu yake neman nono."
Ban ce komai ba na kar'be shi na zauna gefan Hajja wadda suka ta hirar duniya da Ya Falmata tana ta basu labarin rikici da masifar tashin hankalin da aka shiga a maiduguri lokacin farkon boko haram.

Khalil na sanya ya d'auko mini wayata a d'aki na kira Fati na ce su zo gabad'aya za su gaisa da maigidan. Ta ce mini abinci suke ci da sun kammala za su zo.....✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*162*
Ganinta a zaune ya sanya na share kawai ban kai masa abincin ba idan ya koma gidanta sai ta bashi abinda taci su kwanta duk rashin moruwarta da yake fad'i ai ba zata kwana da yunwa ba.
Na ji tana magana da Hajja kan zuwa inna Uwani gobe wai sun yi waya Hajjan ta bata amsa da cewar itama ta sanar da ita.
Ya sauko cikin mutunci da kulawa ya zauna a falon bayan shigowarsu Fati gabad'aya ya gaisa da su har yana jan su Hassanar gidanmu da tsokana haka dai suka dinga sinne kai irin na rashin sabo yadda ya zauna ya kula su shine abinda ya d'an sassauta mini zuciyata domin kuwa ko babu komai bai 'kyamace su ba ya nuna suma cikakkun mutane ne masu kima da karamci zuwansu ya sanya shi farinciki har yana mik'a godiyarsa wannan yana daya daga cikin kyawawan halayensa karrama mutum duk rauni da rashinsa baya ta'ba nunawa na 'kasa da shi cewa shi ba komai ba ne, fuskarsa a sake zai mu'amulanci mutanan da ya tabbatar da cewa ya fi suttura da rufin asiri.
Mun d'an jima tare da shi a falon da su ma gabad'aya kafin ya yi wa Hajja sallama ya fita. Jim kad'an itama ta tashi ta bi bayansa bayan ta yi mana sallama kamar dai gaske ta saki jikinta tana walwala tamkar babu komai a zuciyata Hauwa kenan .
Yusi kuwa kam ganina da shi biyu tunda suka zo yana can tare da Adamu sai da gari ya waye tukkuna suka shigo su biyu da akwatina hud'u jiyan ba su samu damar kawo kayan ba.
Muna d'aki gabad'aya anti Yagana Ya Falmata da Sahura. Yusra tana bacci saman kujera bata tashi ba.
Na bi su da ido har suka gama shigo da akwatinan kayan suka ajiyesu a gefe ban ce komai ba.
Muka gaisa da su suka zauna cikin nishadi da jin dad'in had'uwa da juna wannan so da k'aunar da suke yi wa junansu har mamaki yake ba ni.
Hassan na hannun Adam Usaini shi kuma yana hannun Yusi na ji shi Adam din yana fad'in." Mama Baba ne ya ce mu kawo miki kayan nan akwai wasu kayan ma da za mu d'auko da yamma anti Nabila ta ba ni lambar wayar direban idan suka iso zai kira ni."
A takaice na ce." To shikkenan."
Ya mi'kawa anti Yagana yaron da yake hannunsa ya riga Yusi fita shi yana zaune kamar akwai magana a bakinsa na dube shi ina fad'in." Kai ma ka zama munafiki ko?"

Ya dube ni da sauri yana fad'in." Munafiki Mama?" Na gyad'a kaina ban ce komai saboda takaici to bayan wad'annan kayan akwai wasu kenan.
Ya Falmata ta b'ata rai tana fad'in." Menene abin munafurci Amina."
Na ce." Haushi yake ba ni wallahi idan yana yin wani abin Ya Falmata yaron nan baya goya mini baya ya manta da ni ma gabad'aya."
Ta kama dariya tana fad'in." To yanzu me ya faru da kike barar goyan baya daga gare shi a da can fa shine shalele ko don yanzu kin samu wasu shine za ki cillar dashi."
Na ce." Shi ya fara cillar da ni ai Ya Falmata."
Murmushi ya yi kawai bai ce komai ba ya mika mata yaron yana fadin." Bari na je na same shi Mama zan dawo sai mu yi magana ko idan na yi lefi a yi hakuri.''
Hararsa na yi yasa dariya da sauri ya fice. Sahura ta fito daga toilet wanka ta yi ta ta zauna tana shafa mai. Na dube ta a hankali wata irin ki'ba ta yi zamanta a gefena da d'aurin kirji na sake gazgatawa na ce." Wai ke maganin ki'ba ki ka sha ne?"
Anti Yagana ta ce." Kin riga ni magana Amina na ce ko idona ne yake yi mini gizo ne."
Dariya kawai take yi tana fad'in." Kwanciyar hankali ne kawai. Ya Falmata na fad'in idan haihuwa ma ta tsaya ana samun canji irin haka."
D'akin ya d'auki shiru na wani lokacin na dubi anti Yagana ina fad'in." Wai ya kuka yi da maigidan nan ne?"
Ta yi shiru tana d'an kallona kafin ta ce." Na same shi ne domin na yi masa godiya bisa abinda ya yi miki na alheri da farko na yi tunanin ke kad'ai ya ware ya bawa tare da yaran nan sai daga baya kuma da yayi mini bayani na gane dalilinsa wallahi abin ne ya ba ni tsoro Amina shiyasa na gaza ha'kuri na ce bari na yi magana akai saboda ina jin tsoron k'aramar magana ta zama babba a zo ana ta maganganu marasa kyau a kan ki."
Ya Falmata ta b'ata rai tana fad'in." Akan wane dalili za ki tare shi da wannan maganar Yagana kin yi kuskure anan gaskiya tunda ta zo ta gaya mana na ce ta kar'ba tunda ba ita ta ro'ka ba shi ya bata. Amina mahad'in arzikinsa ce don ya dauki 'karamin kamfani ya bata bai nakasa kansa ba kuma yana da ninikin abinda ya bata din amma shine ki ka zame jiki ki ka tare shi ba ki ji nauyi ba don Allah Yagana."
Ta gyad'a kanta tana ce wa." Ni fa ba da wani abin na yi masa magana ba Ya Falmata kin san irin haka yana haddasa rigima tsakanin iyali ki ga gida ya rikice ana ta fad'a kuma da yawa wasu mazan sune suke asassawa wajan fifita wani bangare.
kuma ba ita kad'ai ce matarsa ba Hauwa yar uwarsa ce kuma matarsa itama tana da yara tana kuma da hakki."
Ta ce." Lokacin da zai yi mata kyauta kin sani ne Yagana? ke dai ba yar uwarki ki ka sani ba me yasa ba za ki goya mata baya ba bisa abin alherin da ta samu kin ga kenan anan gaba zaki sanya masa shakku idan ya yi niyyar yi mata wani alherin."

Ta yi shiru bata ce komai ba.  Na gane dalilinta na magana kuma tana da hujja amma yanzu tunda ya fito ya fad'i da bakinsa ni ya bawa ba yara ba shikkenan.
Na ce." Ya ji haushi har yana ta fad'a wai babu wanda zai nuna masa yadda zai yi da abinsa. Ya gaya mini dalilai masu muhimmancin da ya sanya shi ba ni kyautar wannan kamfani. Na kar'ba kuma na gode amma abinda na yanke shine ya sanya mini shi a kasuwa a kar'bi kudin domin idan har zai cigaba da aiki da sunana akwai matsala babba a tashe shi daga aiki idan ya so na nemi plaza na saya na fad'ad'a harkokina na kuma sanya haya a wasu wuraran."
Ya Falmata da annashuwa ta furta." Wannan tunanin naki ya yi  Amina. Ya kike gani Yagana hakan ya yi ko?"
Ta furta." Ya yi sosai Ubangiji Allah Ya dafa miki amma ta wace sigar za ki tunkare shi har ki gaya masa ya sa a kasuwa ya baki kudin."
Na furta." Ni ma ban san ta sigar da zan gaya masa ba wallahi tunda yanzu fad'a yake ta yi kan cewa ba ya yi mini gwaninta duk abinda ya yi mini na alheri sai na gwasile na ce ga yadda nake so."
Sahura da ta gama sanya kayanta kuma tunda muka fara maganar ba ta ce komai ba sai yanzu ta furta." Sister na taya ki murna sosai Ubangiji Allah Ya yi ri'ko da hannunki lallai kin cancanta da fiye da abinda ya fi haka ma, an yi gwagwarmaya kuma an tari kalubale mabambamta amma ni a shawarce ki bari a kwana biyu lokacin da kuke dad'i da shi sai ki gaya masa tunaninki idan kin ci sa'a zai amince tunda gaskiya yana da sau'kin kai a wasu lukutan."
Anti Yagana ta ce." Ni ma tunanin da na yi kenan ki bari a kwana biyu kun samu nutsuwa dake da shi cikin lumana sai ki gaya masa abinda ki ke so."
Na sauke ajiyar zuciya a hankali na furta.''In sha Allah."
Yusura ta tashi daga bacci ta shiga toilet ta fito na ce ta janyo mana akwatinan kayan nan.
Ta d'auko su d'aya bayan d'aya aka bud'e kaya ne masu kyau da kud'i kuma ta duba quality sosai babu wani k'aramin abu a ciki ko na son zuciya ban san dai iya adadin kud'in da ya bata ba amma ta yi kokari kuma sun yi kyau kayan kwarai
Muka gani gabad'aya Ya Falmata 'yar gayu mai son abu mai kyau sai yabawa take yi da kayan. Muka gama gani yarinyar ta mayar da su inda suke. Gaza ha'kuri na yi na sauke ajiyar zuciya ina duban anti Yagana na ce." Nabila ce fa ta had'o kayan nan."
Ta yi kasa'ke da alama ba ta gane Nabilar da nake magana akai ba Sahura ta yi caraf tana ce wa." Nabila wadda na sani 'kanwar Hajiya Maryam mai rasuwa."
Na gyad'a kaina ina kallonta. Anti Yagana da sauri ta ce." Kamar Yaya dama ba shine  ya sayowa yaran ba?"
Na ce." Kudi ya bata ta sayo musu anti Yagana mu zube lamarin nan a fefe mu kuma aunashi da ma'auni na hankali da adalci shin me kuka fahimta don Allah?"
Ya Falmata ta yi shiru domin bata san bada'kalar da ta faru ba fadi take yi aikuwa kaya dai sun yi kyau Amina ina ganin ko ke ce abinda za ki sayo

kenan domin dai babu abinda babu kuma kowacece wannan ba ta yi cuta da almundahana ba
Anti Yagana ta ce." Ba ki gane ba ne, ita wadda ya bawa kudin kayan k'anwar wannan matar tasa ce fa Maryam da ta rasu mahaifiyar yaron nan Adamu da suka kawo kayan tare da Yusi."

Na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Ta d'an yi shiru na wani lokaci sai ta ce." Ba ta da aure ne?''
Ta gyad'a kanta tana fad'in." Bazawara ce tana zaune gidan yayarta tana business da kuma kula da yaran. Shi babban ma Salim baya gari ita kuma Nusaiba tun iyayansu na raye suka yi mata aure sai shi wannan karamin Adamu."
Na ce." Yana ta jaddada mini cewa business d'in da take yi kenan kuma da a sayi kaya a waje gwara a saya a wurinta. Ke anti Yagana kin san wuya da masifar da muka shiga dalilin Maryam ko, me kike tunanin zai faru yanzu tunda shi ba shi da tunani bai gane cewa sonsa take yi ba."
Ta dinga girgiza kanta tana fad'in." Lallai mutumin nan to ina ruwansa da ita idan ba yana so ya d'auka ba shi yanzu don girman Allah sai ya yi zawarcinta duk matan da suke duniya."
Ya Falmata ta yi shiru fuskarta ta canza da wani yanayi ta ce." Wata'kila wannan kyautar da ya yi miki yana so ne ya kashe miki baki kin ga ai idan ya yun'kuro domin auranta baki da bakin magana to mutumin da aka bawa kamfani na miliyoyin kud'i. Ai ya jefi tsuntsu da dutse biyu ne.
Zuru na yi ina kallonta Ya Falmata macace mai tsinkaye sosai ni ban ma ta'ba yin wannan tunanin ba, amma har yanzu zuciyata bata gama aminta da cewa zai iya yin zawarcin Nabila ba idan an yi duba da irin muguwar wahalar da muka ci domin dai ba shi kad'ai ya shiga tasku ba har da mu gabad'aya Allah ne ya sa da kwanansa a gaba.
Anti Yagana ta ce." Hakan za ta iya kasancewa ya yi da wannan niyyar ne, amma abin ya ba ni mamaki wallahi, wai me yasa wasu mazan ba su da tunani ne?"
Sahura ta furta." Sai ki tsananta da addu'a Amina ni kaina wallahi na tsorata wad'annan mutanan sai kace mayu ita ta yi ta gama ita kuma wannan zata kutso kanta ba wani abu ta hange ba sai dukiya ce sun zama annoba wallahi.
Anti Yagana ta dubi Ya Falmata da mataccen jiki ta shiga bata labarin irin abubuwan da suka faru baya kafin rasuwar Hajiya Maryam din.
Ta dube ni tana fad'in." Ki ajiye kayan kada ki yi wa yaranki amfani da su. Ya bada wasu kudin kafin mu tafi mu sayo musu sannan ko ya ba ki takardun kamfanin nan kada ki kar'ba har sai ya gaya miki abinda yake tsakaninsa da ita irin wannan fa sai dai ki ji an d'aura tunda haka ya yi lokacin auran 'yar uwarta."
Shiru kawai na yi ban iya cewa komai ba. muka yini muna tattauna lamarin shima tun jiya da daddare da ya fita bai sake shigowa ba. Sai bayan la'asar duk muna falo yaran suka sake shigowa a karo na biyu wannan karon har da

Masa'udu kowanne kafad'arsa sa'be da dilar atamfa suka jibge dila biyar a gefe sai wasu manyan kwalaye hud'u da suka shigo da shi suka tattara kayan waje daya.
Suka fita jim kad'an Hauwa da inna Uwani har da yaran gabad'aya suka shigo a gidanta suka yini, alamu sun nuna itama Inna Uwanin bata jima da sauka ba kuma kai tsaye gidan yarta ta sauka. Hakan kuwa ya bawa Hajja haushi domin a takaice ta amsa gaisuwarta yayin da ita kuma take ta washe baki da Hasan a hannunta tana yi mini sannu da barka da arziki ina amsawa tare da kallonsu daga ita har Hauwan nema suke yi su mayar da mutane shashasai
Jim kan da zamansu shima ya shigo ganinsa sanye da kayan shan iska irin wanda ya saba sanyawa idan yana gida
ya tabbatar mini da cewa bai fita ba gabad'aya amma bai shigo ba sai yanzu. Ya zauna a ka shiga gaisawa nan na ji yana gayawa Hajja bacci ya yi tun safe shiyasa bai shigo da wuri ba. Ya Falmata ta fara tashi ta shiga d'akina. Da kamar minti goma anti Yagana ta bi bayanta Sahura da Yusura dama suna ciki ba su fito ba. Sauran kuwa suna can sashen ba'ki tun safe da muka gaisa na ce su koma can su yi zamansu sai sun fi sakewa.
Ni ma ban yi dogon zama ba na tashi na bar musu yaran gabad'aya. Ina daf da shiga d'akina mai sunan Mamana ta fito Hajiya Saratu kenan da yake d'akin Hauwa na da suka sauka ita da Hajja tunda asali d'akin da suke yada zango idan sun zo Khalil ne a ciki yanzu ta tsaya cikin raha tana fad'in." Uwargida kuma uwar biyu sau biyu." Dariya na yi na ce." Hajajju kenan ina yini." Ta amsa da kulawa tana fad'in." Na ce bari na fito nasan yanzu Falmata tana nan ta fara bada labari."
Ina dariya na furta." Yanzu kuwa ta shiga d'aki yau tun safe bata jin dadin jikinta zazza'bi ne amma ta sha magani da sauki."
Na fad'i mata hakane kawai domin ban san abinda zan ce mata ba bayan haka dalili tunda suka zo ake yin wannan zaman a yi hira a yi wasa da dariya amma tunda na gaya musu abinda yake faruwa jikinsu ya yi sanyi mussaman ita din. Kishi ne da su haka Mamanmu take da wannan kishin da rashin son kishiya yanzu nan duk sai su damu. Gashi dai ba ita za a yi wa ba jin labarin wahalar dana sha a baya ya sanyayyar mata da jiki gabad'aya ma kyautar da take ta murna an yi mini ta daina burgeta don tunaninta yana gaya mata danne mini kirji zai yi kawai sai dai mu ji d'aurin aure.
Na shiga d'akin na samesu suna sake tattaunar maganar Ya Falmata duk ta yi wani kicin-kicin da rai na ji tana fad'in zaman ya isheta yau kwana bakwai tunda yara sun amsa sunansu su yi shirin tafiya kawai.
Na zauna gefanta ina fad'in." Wane irin tafiya kuma Ya Falmata ku bari a kàrasa shagalin sunan mana.
Tsaki ta ja kafin ta ce." Mijinki haushi yake ba ni Amina wallahi sam shekarunsa ba su amfanar da shi komai ba gabad'aya ba shi da tunani da hangen nesa."
Dariya ce ta kama ni ganin yadda ta hak'ikance tana ta fad'a.
Na shiga wanka na fito na shirya jikina sosai d'aya daga cikin sabbin d'inkunan da na yi wanda Sahura ta zo mini da su.

Still dai maganar suke yi anti Yagana tana fad'in." Wata'kila ma ita ya bawa kudin raggon suna tunda yau da ake da kwana bakwai a al'ada ya kamata a ce an yankawa yara rago duk da ba a ce dole yin hakan farilla ba ne.
Waya ta yi kara tana can saman dirowa kusa da Sahura ita ta miko mini don yadda ake ta caccakar ubangidan nata bata iya sanya baki ba yanayinta dai da yar damuwa itama abin ya bata haushi da mamaki.
Na d'aga wayar cikin nutsuwa ya kira yi sunana na amsa ya ce." Ki zo ki same ni mu yi magana ina sama." Na ce." To shikkenan." Ya kashe waya ni ma na kashe tawa.
Suna falon Hajja Inna Uwani da Hauwa da kuma mai sunan Mamana suna ta hira Hajja yanzu ta sake da 'yar uwarta. Sannu na yi musu na d'an tsaya muna magana da ita akan farin kwalli wai ta sanya Magaji ya nemo a can kano din ya kawo had'e da garafuni na ce to shikkenan an gode.
Ina kallon Hauwa tana d'an satar kallona domin ni kaina nasan na yi kyau sosai atamfa ce a jikina amma duk jikinta aiki ne da uban stones ko ta ina dinkin buba ne ya zauna a jikina yadda ake so.
Na haye saman zuciyata sam babu dadi ina kallon tarin kayan da su Adam suka jibge wajan 'kafar benan zan dai ji dalili.
A zaune na same shi yana waya aikin kenan na zauna har ya gama ya juyo tana kallona tare da kiran sunana.
Na sake amsawa ni ma idonsa a kaina. Ya cigaba da cewa." Ki yi hakuri yau tun safe ban shigo ba kin san Allah bacci ne ya shammace ni  mai nauyi na ce da Hauwa ta tashe ni kafin azuhur wai ta manta sai uku da wani abu na tashi sallah sai a lokacin na yi."
Na yi shiru ban ce komai.
Ya ce." Na so yau a yi wa yaran nan yanka hakan bai yiwu ba amma gobe idan Allah ya kaimu za a yi da wuri akwai shanu biyu wannan na jama'ar da suke kewaye damu ne ku d'iba Hajja ma ku bata nata ku bawa Hauwa da duk wanda yake da hakki. Ragona hud'u ne wannan naki sai kin ga dama za ki ba ni."
Ya fad'a yana kallona na daure zuciyata na ce." To an gode Allah Ya saka da alheri da budi."
Ya ce.'' Ni ne da godiya ranar juma'a mai zuwa kuma za mu yi walima kamar dai yadda na saba abokaina da Malamai za su halarta in sha Allahu rabbi za a yi adduoi kamar yadda annabin rahama ya koyar da mu. Ubangiji Allah Ya raya mana zuria."
Na sake amsawa da Amin Ya Allah.
Ya yi shiru na d'an wani lokaci kafin ya cigaba da cewa." Duk abinda za a buk'ata fannin ci da sha za a yi order babu buk'atar a wahalar da wani sai dai akwai turaman atamfofi da Nabila ta yi mini tallansu gasunan na saya miki ki rabawa jama'arki."
Na sake godiya a ta'kaice kafin na ce.'' To abinda yake cikin kwalayen fa."
Ya d'an yi shiru kafin ya furta.'' Zannuwa  kawai na saya a wurinta amma bari mu gani."

Ya fara neman lambarta tunda wayarsa dama tana hannunsa bugu d'aya ta shiga ta d'aga na ji suna gaisawa ya ce." Bayan zannuwan da na saya menene ki ka aiko yara da shi a akwali?"
Shiru ya yi yana sauraranta da yake can k'asa take magana ban ji komai ba. Sai da suka yi sallama tukkuna ya dube ni yana fad'in." Kin ji gudumuwa ta yi mana wai abin rabo ne duk wanda a ka bawa zani sai a sa masa cikin jaka mun gode ko?"
Na ce." Ka gode dai ai kai ta yi wa ba Amina ba. Ya yi shiru yana kallona na cigaba da cewa." Ka ce da ni soyayya kuke yi ba wai ka zaunar da ni kana kwantar mini da kai ba. Soyayya kuke yi a fakaice ka yi mata alheri ta yi maka zaka maye gurbin Maryam da ita ko ba haka ba ne."
Ya gyad'a kansa yana cewa.'' Sai ta iya kasancewa hakan ne amma ana ta 'bangaran fa wata'kila sona take yi."
"Kai kuma da ka gane hakan sai ka cigaba da biye mata tunda kana hangen jin dadi da nagarta a tattare da ita ko?"
Ya yi banza da ni kawai ya mike 'kafarsa ya kwanta tare da lumshe idonsa.
Na ce." Wallahi tallahi wannan abin ya ba ni mamaki da tsoro yanzu kai ba ka jin wani iri a jikinka.
Ya bude ido yana dubana kafin ya furta." Ba ni jin komai, kuma ba zan yi rigima dake ba a cikin mutane Nabila dai idan za ta sare kanta ta ba ni shi saboda so wallahi ba zan aureta ba. Idan kun ce tana sona ba zance a a ba, amma ni fa ba ni sonta ba kuma ni da niyyar auranta. Wannan maganar idan ba ku daina yi mini ita ba daga ke har ita Hauwa wallahi sai ranku ya 'baci tunda babu wadda ta haife ni a cikinku ina dalili ne za ku dame ni da wata Nabila."
Na ce." Kai zaka daina idan har kana so a daina yi maka maganarta cikinmu babu yaro k'arami da za ka yi wa wasa da hankali."
Ya furta." Zan daina amma ba zan wula'kantata kamar yadda kuke so ba wallahi, idan zan nemi aure a cikinku akwai wadda ta isa na yi wasa da hankalita, abinda Allah da Annabinsa suka halasta mini me yasa zan ji tsoron wata hallita wadda take da rauni kuma take a k'arkashin ikona........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK.*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*163*
Share shi na yi ban 'kara tanka masa ba ba kuma don ba ni da abinda zan ce ba. Na tashi na sauka k'asa jikina babu wani karsashi ya rantse da Allah ya kara rantsuwa ba zai iya auranta ba to yaudararta zai yi kenan tunda shi ma zuwa yanzu ya gane sonsa take yi muddin bai fito fili ya nuna mata baya ra'ayinta ba za ta cigaba da bibiyarsa da zaman saurare daga gare shi tunda yana sayan kayanta yana kuma bata kudi yawanci mu mata wayayene shi yanzu ga abinda yake cikin zuciyarsa a game da ita duk da ba wai ya bankad'a mini zuciyar tasa ya yi na gani ba amma dai akwai k'amshin

gaskiya a maganarsa don da ya na sonta da niyyar aure ba zai yi rantsuwa da Ubangiji ba tunda ya san girmansa. Shirunsa da yanayin yadda yake mu'amulantarta shine abinda zai k'ara mata kwarin gwiwa ta ji a ranta kamar buk'atarta za ta biya domin samun nasarar mallakarsa duk abinda take yi a kansa da wanda ya dangance shi sone ba wani abu ba.
Bandir din atamfofin irin mai sha biyu ce bandir shida kuma mabambamta ba duka iri daya ba ne, sun yi kyau sosai duka cotton irin 'yan dubu goma nan ne da ake ya yi idan za a yi ankon biki.
Duk abinda ya kamata da a yi na al'ada da fita hakki su anti Yagana sun yi hatta da atamfofin sai da suka d'ibarwa Hajja nata duk da ba ta yi wata gayya ba amma ai tana da jama'a a can garin Dambatta idan ta koma gida sai ta raba. Nama kuwa da aka soya zallar tsoka da yawa suka zuba mata cikin fanteka  tace ya yi yawa Hajiya Saratu ma kad'an ta d'iba yayin da inna Uwani ta yi kamar ta dora hannu aka ta dinga rusa ihu ganin yadda Hajja ta ce da masu aikin su kwashe nama ta d'ibi daidai gwargwado. Hauwa d'anye ta kar'ba ba ta bari an soya ba ita kuma Inna Uwani koda anti Yagana ta nuna mini wanda ta zuba mata na ce ya yi kad'an ta 'kara ashe duk da haka ba a yi mata gwaninta ba ta ji haushi sosai saboda Hajja bata kar'bi naman da yawa ba ta bawa masu aiki.
Su kansu su anti Yagana sun samu soyayyan nama sosai fatar shanun na sanya aka gyara musu (Ganda) da kawunan suka d'iba Sahura ma ta d'ibi daidai gwargwado sannan sauran na sanya baba Tabawa zubawa a buhu biyu yan gidanmu Ummansu Hadiza gabad'ayansu dai da suka zo tare na ce idan sun je sai su yi rabon a tsanake a tamfofi kuwa kowacce sai da ta tsira da turmi shida duka cikin kowane bandir sai da kowa ya samu har da ragowar wasu. A ranar da muka yi walima k'warai na samu alherai masu yawan gaske daga wurin manyan mutane daga cikin abokananse da suka samu.  Kud'i kaman sai godiya yara sun samu kaya masu yawa. Babu shakka kowace haihuwa da goshinta don haka ni dai ba ni da bakin magana sai dai godiya ga Allah.
Washe gari masu aiki na ta hidimar gyara gidan ciki da wajensa. Su anti Yagana na ta had'a kaya don 'yan gidanmu ma su Ummansu Hadiza da sassafe suka d'auki hanya bisa bin umarnin Babanmu ya ce su taho lallai shi kuma maigidan ya yi musu shirin tafiya cikin mutunci da rufin asiri don da ya ji a motar haya suka zo ya yi fad'a sosai har yana cewa lefina ne nasan za su zo mai yasa ban gaya masa ba tun daga can ya sanya a kawo su ya fi nutsuwa.
Sahura na ta gyara mini wardrobe ita kuma Yusra na shiryawa yaran kayansu.  Hauwa ta aiko Khalil wai na bata atamfa turmi bakwai jin haka Ya Falmata ta fara fad'in ba a d'ibar mata ba dama."
Sahura ta ce." Ni na d'ibar mata turmi shida cikin kowane bandir na d'auki daya."
Ta ce." To kuma wace atamfa za a bata."
Anti Yagana ta ce." Tunda da akwai a bata mana wata'kila wani zata bawa."
Yaron ya ce." E, na ji suna magana da inna Uwani za ta tafi da su can bauchi ta yi rabo."

Ya Falmata ta dube ni tana ta'be baki ban ce komai ba na ce da Yusura ta d'ebo abinda suka rage saura turmi sha uku gabad'aya na ce a cire bakwai din da suka buk'ata a bashi ya kai mata.
Bayan fitarsa Ya Falmata ta kwashe ragowar kaf katon kwalin da suka shirya kayansu a ciki ta watsa atamfofin tana fad'in." Ke ma kina dangi idan mun je gida za a ba su ke da haihuwa wata da iko da kayanki idan haihuwar biyu banza ne ta yi zuciya ta yi."
Sahura ta dinga dariya tana fad'in." Wallahi baiwar Allah nan Hajja tana burgeni suruka ce tagari babu ruwanta da sa ido akan duk abinda yake faruwa ki ga dai uban naman da a ka bata ta dibi kad'an ta bayar da shi. Hauwa da mamanta sai ka ce mayu ita tsabar rashin yarda ma d'anye ta sanya a ka kai mata gida kamar ita ta haihu."
Anti Yagana ta ce." Abu dai ya wuce alhamdulillahi an tashi lafiya wata matsala dai ba ta faru ba ni na gaji ma da zaman nan wallahi Ya Falmata tunda mun had'a kaya an jima muna yin wanka mu kama hanya."
Na ce." Sai dai gobe tunda ya fita kuma har yanzu bai shigo ba ai ba za ku tafi ba tare da kun yi masa sallama ba."
Ta ce." Bashi muke bin sa da sai mun jira ya dawo Amina."
Na ce." Duk da haka dai anti Yagana a bari ya dawo din ya fi mutunci."
Ta yi shiru ba ta sake cewa komai ba. Itama Ya Falmata din ba ta tanka ba maganar dai da take ta jaddada mini shine kada na yarda ya auri Nabila domin babu haske a cikin al'amarin. Yadda ta zafafa sosai abin har mamaki yake ba ni, kishi take taya ni sosai Hauwa ma don dai tana ciki ne muna tare da yaranta babu yadda za a yi da ita.
Ba su tafin ba kuwa sai da gari ya waye tara na safe sun fito lokacin Masa'udu ya kwashe kayansu tsaf ya kai mota su Hajja na d'aki ba su fito ba muka shiga tare muka same su ashe inna Uwani a gidan ta kwana duka muka gaisa cikin mutunci da raha. Ya Falmata tana fad'in." Bako zai yi halinsa Hajja mun yi shirin tafiya, mun gode sosai Allah Ya kara girma yara kuma Allah Ya raya su."
Ta dinga amsa da "Amin mune da godiya Allah Ya saka da alheri."
Tare da ni su gabad'aya muka yi musu rakiya bakin mota suka shiga Ya Falmata da anti Yagana ita Sahura sai gobe yadda muka yi da ita za su tafi.

****

To sati uku da haihuwa gidan na mu ya daidaita kamar ba a yi wata dabdala ba kowa ya watse an bar ni da yara da masu aiki kamar yadda muke a da. Hassan da Usaini basa zuwa hannuna sai idan yunwa ta kawo su suna can wurin Baba Tabawa da taburni da daddare ne kawai nake kwana tare da su, shima maigidan muddin ranar girkina ne sai dai ya sakko kasa ya same ni a d'akina.
A tsukin suka tafi saudiya umara shi da Khalil kamar yadda ya fadi ranar dana haihu. Sati biyu suka dawo a cikin satin kuma ya sabunta mini komai na gidan tun daga kasa har zuwa sama komai sabo da sabbin kayan kicin abin dai kamar wata sabuwar amarya. Hatta da kayan da yara suke sanyawa sai da aka fitar da su aka yi musu sabbi Taburni da Mairo sune masu iyali a

kauye Kuma sune masu wahala da yarab na ce su kwashe suka kuwa cika manyan bacco suka ajiye da jiran lokacin ziyara tunda sun ce sai sallah za su ganin gida yanzu muna daf da shiga wataran Ramadan kuma a watan dai za su tafi umara in sha Allahu rabbi.
Tun bayan watsewar kowa Hauwa ma ta d'auke kafarta tun ma dai washe garin ranar da muka yi walima ba ta sake shigowa ba, hakan bai wani dame ni ba dalili nasan dama abin ba d'orarre ba ne. Na ma yi mamaki sosai da ta iya jurewa a yadda na santa da tayar da fitina har aka gama wannan kacaniyar ba ta ce ga abinda aka yi mata ba.
Shi kuma daga nasa bangaran babu yabo babu fallasa ya ce muna damunsa da maganar Nabila zai fita daga harkar kowacce domin da akwai abubuwan da suke gabansa ba mu isa mu raba masa hankali ba. Da gasken ne sabgogi sun yi masa yawa domin tunda suka dawo daga umara shi da Khalil bai fiye zama a gida ba. Ya je Kano kusan sau uku a kasa da sati hud'u. Ba ma shi da lokaci sosai idan ya dawo da daddare ya ci abinci ya dinga lissafi kenan yaran ba kasafai yake zama da su sosai ba, na yi wankan tsarki tuntuni amma bai lura ba saboda abubuwan da suka sha kansa a tunaninsa har yanzu ina cikin jinin 'biki bai ta'ba nema na ba sai dai 'yan ta'be-ta'be kafin a kwanta.
Order na yi daga kano wurin GARKUWAR MATA 08089965176  package irin na masu jego na ce ta had'a mini na aminta kuma na gazgata sahihancin maganinta shiyasa ba ni shakka da shakku a ko'ina zan yi mata TALLAH da k'umaji da karsashi. Ta kuwa yi mini delivery har garin Abuja na sanya Masa'udu ya je ya kar'bo komai cikin girma da arziki nannad'e da salatif. Na durfafi gyara jikina domin bahaushe ya ce wai idan kana da kyau ka kara da wanka.
Yau da yake girkina ne baya gari ya tafi kano Amma ya ce lallai a gida zai kwana. Na yi tatul ta ko'ina kuma buk'ata na ke ji. Sosai yau kwana hamsin da shida da haihuwa na dawo Amina sosai
 Ado da kwalliya na yi mai kayatarwa don an sake yi mini wani sabon lallen ma baya wanda aka yi mini na bikin suna ba. Sai yanzu na sake gazgata alfanun raba gida hankalina a kwance yake sosai a yanzu Hauwa na can gidanta ni ma ina nawa duk ta ta zame mini jiki amma wallahi watarana har mancewa nake yi da ita mussaman yanzu da muka sake yaiwata a gidan ko ta ina babu kad'aici akwai kuma fahimta mai kyau da masu aikina muna girmama juna

Na kudi ne littafin nan kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

 mutuntawa tabbas da maza da yawa za su gane jin dadin da kwanciyar hankalin da yake tattare da rabawa iyali mazauni da dayawa ba a sa samu rikici da rabuwar kai ba. Khalil ne yakan d'an je gidan jefi-jefi wataran kuma idan babu makaranta ya ja 'yan uwan su je su d'an zauna mata babu kuma wata matsala da ta ta'ba faruwa dalilin zuwansu nasu domin yadda na fahimta so take itama ta ja su a jiki  ta samu irin soyayyar da suke mini har sultan yanzu ya daina tsoronta da shi suke zuwa idan za su tafi hakan yana

yi mini dadi sosai yaro ne Khalil amma mara mantuwa shiyasa ake cewa idan za ka yi sharri ko wani abu na rashin kyautawa kada ka yi a gaban yaro dalili baya mance abu. Yanzu da ya fara girma ya gane cewa mamansa itace matsalar gidansu gashi a aikace cikin hikima yana ta ko'karin ganin ta gyara ta dawo mutuniyar kirki tunda ba zai mance abubuwan da suka dinga faruwa ba.
A bakin yaran nake jin Ladidi suna yawan kiran sunanta sai da na tambayi yaron wacece ita yake gaya mini mai aiki ce da ta zo daga bauchi sunanta Ladidi take wasa da su tare da yi musu tatsuniya ashe kenan an kawo mata mai aiki wata'kila ma ta jima domin lokacin da ta jibgi danyen naman nan na yi ta mamakin yadda za ta yi dashi Ashe tana da mai yi mata hidima ko tare suka zo da inna Uwani Allah ne ya sani.
Sai dare ya dawo bayan ya yi wanka ya ci abinci ya bukaci ganin yara har saman suka same shi ya kuwa kasance da su na tsayin mintina talatin ana ta gaisuwa masu  hawa jikinsa na yi masu tsokanarsa na yi Usaina ce me jan gemunsa tana fad'in ya yi fari furfurar ce bata iya fadi ba har tana nuna masa sabon kitson hannu da Taburni ta yi musu tana cewa." Ka ga nawa ba'ki naka kuwa fari baba ka goge ya dawo irin nawa." Tana ta jan gemun yana dariya kallonsu kawai nake yi har suka gama ya ce su sauka k'asa zai huta da suka fita d'akin ya rage mu biyu ya ce." Na ga lokacin da zan huta Amina, wallahi jikina ciwo yake mini ga shekaru ga wahalhalun rayuwa."
A takaice na ce." Sai sai shekarun amma kai yanzu har wata wahala kake Sha?"
Ya d'an harareni yana fad'in." A a ba na sha a kwance nake samun kudin tunda mafia nake yi."
Dariya maganarsa ta ba ni na yi a takaice ban ce komai ba sai kallonsa da nake yi masa
Ya yi kwafa yana cewa." Yarinyar nan Nabila nema take yi ta matsanta mini fa wai zuwa ta yi can wajan Hajiya Ayya mahaifiyar Alhaji Ahmadu akan na aureta."
Ban ce komai ba sai Ido mu je dai zuwa.
Jin ban yi magana ba ya sanya ya ja goron numfashi kafin ya furta." Ni yanzu karfina duk ya 'kare kun karar mini da shi bana ji jin zan iya ajiye mata uku a yanzu kuma kowacce tana jira na kwanta da ita ni na fara gajiya wallahi."
Duk yadda na kai ga dannewa sai dariya ta subce mini na ce." Haba kaine fa na ji kana fad'in babu abinda ya fi wannan sabga dadi a duniya kuma sai kace ka gaji."
Ya furta." Da gaske na gaji Amina duk da sunna ce mai kyau ai duk fafutukar da na dinga yi a baya wallahi ina son haihuwa ne, Ubangiji Allah Ya ba ni sai godiya yanzu ma ban ce ba ni so ba ina neman kari ina nufin abinda aka yi a baya yanzu ba za a yi ba."
Na girgiza kaina ina kallonsa kafin na ce." To sai ka ce mata me?"
"Na ce sai na yi shawara tukkuna."
Na yi 'kasa da kaina ban sake cewa masa komai ba saboda takaici wace shawara kuma ya fito fili ya gaya musu gaskiya daga ita Nabilan har wadda

ta yi kamun k'afa da ita tunda babu buk'atar aurenta a ransa babu amfanin yi mata yawo da hankali.
A daran dai wani lamari ne ya kasance a tsakani na dashi mai armashi da wahalar mantawa. Soyayya bata tsufa muddin za mu had'u muka zama tamkar sabbin ma'aurata ah to me za a fasa tunda da rai da lafiyar da kuma sauran kuruciyar shima duk fadi yake yi ai yana shiga hannu ya fara makyarkyata tamkar wani d'an magyaru! GARKUWAR MATA ta gama gigita lissafin attajiri sai ya dawo ustaz a daran yabo da kalaman soyayya a cikin harshen labarci ya dinga zuba a yayin da jikinsa yake tsananin neman abinda duniyar ta ginu a kai. Allah Ya sa mu dace Amin.

***

Kwana biyu haka muka dinga gwangwajewa Muna shan soyayya a kuma wannan lokacin ne dana samu dama na gaya masa bukatata kan kyautar da ya yi mini da farko ya ce a a bai ba ni don na sayar ba yanzu haka ana ko'karin sabunta takardun wajan da sunana don haka babu niyyar sayar da shi a tsarinsa.
Na yi ta ko'karin ganin na ganar da shi nufina ya ki ya ce idan ba ni so kawai na gaya masa ba zai yi mini kyauta ba kuma na canza masa tsari ba ana cigaba da gudanar da abinda ake yi a kamfanin duk abinda ya kama na shiga da fita mallakina ne.
Ganin bai amince ba sai na kyale shi. Da yaje ya yi kwana biyu a gidan Hauwa ya dawo na ce masa ina so ya ba ni rancen kudi tunda dama wanda na samu na wurin larabawan nan suna hannunsa bai sa mini cikin acct dina ba. Babu wata fargaba ya tambaye ni abinda zan yi da kudi kuma nawa nake buk'ata. Na ce miliyan hamsin.
Ya jima yana kallona kafin ya furta." Me za ki yi da su?" Da mamaki sosai a tare da shi ya yi mini tambayar."
Na ce." Kasuwancina zan kawo nan garin zan kama shaguna cikin wuse market na zuba kaya tunda yanzu raba 'kafa ake yi."
Ya ce." Yaushe za ki biya ni?"
Na ce." Mu yi a rubuce shekara uku ko hud'u, in sha Allahu rabbi zan biya ka kudinka."
Ya gyad'a kansa yana kallona kafin ya furta." Ki ce kawai na baki kudi Hajiya kai tsaye amma ai kin san babu rance a tsakaninmu ko?"
Na gyad'a kaina ina fad'in." Da akwai mana idan da yarda da amana ko kana ganin ba zan iya biyanka ba?"
Girgiza kansa ya yi kafin ya ce." Za ki iya tunda me nema ce ke amma ki bari zan yi shawara akan hakan. Zan kuma sanya miki kudinki da suke hannuna."
Na 'bata rai tare da cewa." Tunda sai ka yi shawara za ka ba ni me yasa ba za ka amince da shawarata ta farko ba abin nan ni ka ce ka bawa to me yasa ba za ka bari na yi iko da shi ba ashe kyautar ba har zuciyarka ka yi mini ba tunda ka hana ni na yi iko da shi."
Ya furta.'' Ai ni ban baki don ki sayar ba, kin ga kuwa babu wani dalili da zai sanya ki ce mini na ba ki umarnin sayarwa, amma dai yanzu tunda na ji

hanzarinki ki bari na yi tunani tukkun ko an gaya mini haka ake tafiya kai tsaye komai yana buk'atar nazari da tunani."
Shiru na yi ban sake yi masa wata magana ba, muka cigaba da tafiya a haka shima bai sake  tashin maganar ba ya kuma sanya mini kudina da suke hannunsa kamar yadda ya fad'a.
Ranar wata lahadi da sassafe na hau saman na same shi da yake a d'akina nake kwana wataran ya biyo ni mu kwana tare ranar da yake da ayyuka kuma ko ya biyo ni yana fita idan muka kammala uzurinmu.
Na same shi suna bidiyo call da Kamalu shigowata d'akin na ji yana fad'in."
To ga tanan ma ta shigo Amina zo ga  Ustaz sunan da yake kiransa da shi kenan tun lokacin da ya dawo daga makarantar horon da muka kai shi ni da Hamusu.
Na zauna cike da wani irin farinciki. Tunda ya tafi ba mu gaisa ba kusan wata uku da wani abu bana jin ma sun yi magana da Hajja don da sun yi din za ta gaya mini......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*164*
Mama ya kuke ina fatan duk kuna nan lafiya."Na kasa 'boye murnar ganinsa cikin suttura da nutsuwa tare da wata iriyar kamala ta mussaman na amsa idona a kansa. Lallai Ubangiji shine isashshe idan har mumini ya yarda da kaddara da jarabta ya kuma kar'bi abinda Allah ya wanzar a rayuwarsa tabbas hakuri da tawakallin da ya yi zai haifar masa da wani irin farinciki da murmushi na mussaman daga wajan Ubangiji.
Yana zaune yana kallonmu shima fuskarsa a sake da alama ya ji dadin ganin yanayinmu ni da yaron ya dinga murmushi bai dai tofa ma komai ba a cikin maganar da muke yi har muka kammala ya juyo kansa suka yi magana kad'an kafin mu yi sallama gabad'aya ya kashe wayar yana kallona har yanzu da murmushin a fuskarsa idonsa a kaina ya furta." Na jima ban gan ki cikin nishadi irin wannan ba Giwa, ke ko kunya ba ki ji irin ta iyaye da yaransu na fari."
Ni ma da murmushi a fuskarta nake kallonsa haka kawai sai na ji wani bala'in sonsa ya kara ninkuwa a cikin raina. Tabbas da sanya hannunsa da kuma kokarinsa tare da tasirin addu'ar da muke yi Kamalu ya kai matakin da yake a yanzu. Na hangi abubuwa da yawa a tattare da yaron kuma ni ma na yarda bayan wahala sai dad'i kamar yadda da yawa mutane ke fad'in akwai haske cikin lamarinsa ina ji a jikina yaron zai zama abin alfahari gare mu bakid'aya.. Na ce." To ai ni ba mutuniyar da ba ce, addu'a kawai fa na yi masa akwai abinda na yi na rashin kunya bayan wannan?''
Ya girgiza kansa yana kallona bai ce komai. Na kama hannuwansa a hankali na sanya idona a cikin nasa na ce." Ba ni da wata kalma da zan yi amfani da ita wajan nuna godiyata a wurinka. Ka cancanci duk wani abu a wajena na

gode Allah Ya saka da alheri yadda ka tsaya mini akan yaran nan ka ke yi musu wahala da jiki da dukiyarka Ubangiji Allah saka da alheri. Yaranka Allah Ya kula da su."
Ya matse hannuna dake cikin nasa a nutse ya ce." Babu buk'atar godiya a tsakanina dake Amina ni ma ai kin yi mini alheri, kin cancanta kuma abinda ki ka haifa da wani namijin na sha gaya miki ki sa a ranki kamar da ni ki ka haifa, ni ne ubansu har yanzu kuma abinda nake ban yi domin a yi mini godiya ba ina neman aljannata ne."
Na ji idona ya ciko da ruwan hawaye kuma duk yadda na kai ga ganin na hana su zuba sai da suka kwaranyo ina so na yi magana na kasa kawai sai na fashe da kuka.
Ya kuwa ki'dime jikinsa har yana rawa ya d'an rungume ni a jikinsa yana fad'in." Menene kuma abin kuka abinda zai b'ata mini rai kenan me aka yi da za ki yi kuka Amina?"
Na kasa cewa komai saboda maganar ma da yake yi ta sake raunatar mini da zuciya na dinga yi cikin k'aramin sauti ya matse ni tsam a jikinsa yana dago fuskata tafin hannunsa yasa ya dinga goge mini fuska.
Na daure da yar rawar murya na ce." Na dai gode kuma ba zan fasa godiya ba Allah Ya saka da alheri."
Ya yi shiru bai ce komai ba sai shafa fatar hannuna yake yi ya kama hannun ya sumbuta a tsanake ya furta." Godiya za ki yi ga Allah ki kuma ajiye a ranki cewa yaranki ba za su yi maraici ba muddin ina raye.
***
To wannan ya wuce da sati uku muna zaune kalau zuwa yanzu hankalina ya d'an fara kwanciya dangane da lamarinsa da Nabila domin kuwa bayan rantsuwar da ya yi mini tun farko kan cewa ba zai aureta ba ya sake yin wata tare da jaddada mini cewa ko da Allah ya sake k'addara masa aure to ba ya tunanin zai auri mace kamar Nabila saboda a cewarsa ya hangi tarin matsaltsalu mabambamta daga wajenta.
Ranar dana kar'bi girki ya shigo da yamma anan gidana ya yi wanka ya shirya ya ce mini akwai ba'kin da ya yi yanzu zai fita zuwa guesthouse din shi..
Yana tsaka da kimtsa jikinsa Hajja ta kira ya daga suka gaisa da yake handsfree ne duk Ina ji tana tambayarmu da yara ya ce mata kowa lafiya sai na ji tana fad'in. "Ashe neman aure ka ke yi ban sani ba?"
Ya kuwa diririce ya juyo ya dube ni da sauri dalili yana da tabbacin na ji abinda ta ce tunda murya ya bud'e..
Ya nemi gefan gado ya zauna da wayar a kunnansa yana sauraranta ni ma duk Ina jin abinda take gaya masa wato Hajiya Ayya ta je har gida ta same ta maganar Nabila domin a yadda ta yi mata bayani ma tana gaya mata sun daidaita junansu amma shi ya ce mata ta d'an saurare shi sai bayan sallah sai a d'aura auran tunda daf muke da mu shiga wataran azimi.
Ya cika da mamaki ainun gabad'aya yanayinsa ya canza da b'acin rai ya shiga rantse mata da Allah kan cewa bai san da maganar ba Nabila dai tana sonsa tuntuni ya gane amma bai yi mata alkawarin aure ba, duk abinda ta je ta gayawa Hajiya Ayya karya take yi.

Hajja ta ce." To ni dai abinda ta zo ta gaya mini kenan sai nace ban sani ba don baka gaya mini ba amma zan tambayaka na ji shin da gaske ne?"
Ya girgiza kansa kamar yana gabanta ya ce." Karya take yi wallahi ban ce zan aurta ba." Ta ce." Ba ka ce zaka aureta ba amma ka san tana sonka tunda gashi ka fadi da bakinka me yasa ka biye mata har aka yi magana da kai kace za ka yi shawara idan da ni za ka yi shawara to babu yawuna ga mata nan da yawa a gari idan lallai auran zaka 'kara ba zan hana ka ba, domin na fahimci tunda aka samu akasin auranka da yarinyar nan Hajara ka ke ta kame-kame babu yawuna wajan auran Nabila kanwar Maryam domin idan ka manta ni uwarka ban manta ba. Abinda ya faru a baya ba ni fatan ya sake faruwa ba. Idan za ka yi aure ka duba nagarta da cancanta kada kyale-kyale ya rudeka ka jefa rayuwarka a masifa ka jefa jama'ar da suke kewaye da kai. Tunda zuciyar taku a haka ta ginu kuma kana ji kana da kudi za ka iya to sai ka zo nan d'ambatta a duba maka wadda ta dace wadda kuma zata zauna lafiya da iyalinka."
Ya furta.'' Babu ma buk'atar karin aure a yanzu Hajja, kuma in sha Allah yadda ki ka ce hakan za a yi dama ba ni da ra'ayin auranta a cikin raina."
Ta ce." Abinda na gayawa Hajiya Ayya kenan zan tambayeka na ji ta bakinka wata'kila duk bada'kalar da ta faru ba ta da labari shiyasa har ta iya zuwa ta same ni domin na hada jini da dangantaka da zuriar Maryam Allah Ya yi mini tsari da su."
Haka suka yi sallama ta yi masa tas!  Ya kashe wayar yana kallona a hargitse ya ce." Wato duk kara da kawaicin da nake yi wa yarinyar nan ba ta duba ba take bin iyayena har tana fad'in mun tsayar da magana bayan sallah d'aurin aure ni mahaukaci ne Amina?"
Na d'aga kaina alam e amma ban ce komai.
Ya nuna kirjinsa da yatsa yana fad'in." Mahaukaci ne ni ko?"
Shiru ban ce masa komai ba dai ya d'auki wayarsa da sauri yana fad'in." Kin ga ni da idonki na goge lambar wayarta tunda bata da hankali ni me zan ci da yar banza."
Bai goge ba ya sake kallona yana cewa." Kafin na goge yana da kyau na yi mata gargadi ba ni son sakarci da shirme?"
Na ce."Tambayata kake yi?"
Ta gyad'a kansa na furta." Lokacin da ku ka yi serving lambar juna ai baka nemi shawarata ba. Me zan ce maka yanzu duk abinda za ka gaya mata domin ta kiyayeka ka sani ba sai ka nemi shawarar wani ba.
Ya ja tsaki yana fad'in." Dogon rubutun ne ba ni so ai kar'bi ki shiga Whasap din ta ki rubuta mata cewa ba na sonta babu kuma maganar aure a tsakaninmu ta nemi miji daidai da ita ta aura.
Na sanya hannu na kar'bi wayar kamar zan bi umarinsa. Whasap number dinta na shiga ya yi serving da sunanta Nabila. Nan na dinga cin karo da stickas na soyayya da gaisuwar Juma'a iri iri tare da wasu irin wasik'u da kalaman soyayya masu motsa sha'awa irin dai yadda matan bariki ke janye hankalin mazan mutane. Gasu nan birjik kuma idan ta turo yana bud'ewa ya gani amma bai mayar mata da martani ba. Maganarsu da ta d'an yi tsayi

akan tallan kayanta da ta yi masa shine ya kula ta har ya yi mata rubutu a takaice ya ce da ita yana so zai saya.
Kunya da takaice suka hana ni cewa komai na yi kasa da kaina tsabar b'akinciki wasu matan dai rako wasu suka yi duniya. Babban abin b'akinciki da takaici shine ka turawa mutum sako ka tabbatar ya gani kuma yana hawa online bai baka amsa ba gobe ma ka sake tura masa saboda rashin zuciya messages kuma irin na soyayya da nuna kulawa har da fatan alheri amma mutum ya share abin da ciwo sosai amma ita kamar kidahuma mara sanin ciwon kai ko wannan ma kora da hali ne an nuna ba a yin ki a fakaice amma kin nace su kansu wasikun da suke d'auke da zantukan soyayya masu tattare da batsa babban dalili ne da zai sanya ya k'yamaci auranta bayan wad'ancan dalilah masu girma. Duk wayewarsa a gida yake yi a d'aki kuma tare da iyalinsa akwai gogewa a wannan fannin kam yanzu ya yi mata wannan wulakancin tana sake ma'kale masa sautari maza sun fi naci da bibikon macan da take wahalar da su wadda take nuna musu so da k'auna kuma sai su d'auketa sakarai su yi ta wasa da hankalina kamar dai yadda yake yi mata a yanzu ta kasa ganewa.
Na dube shi ina fad'in." Ashe ga dalilin da ya sanya ka kasa fitowa ka gaya mata gaskiyar abinda yake zuciyarka. Tana yi maka irin wannan zantukan na rashin mutunci ai ka ga duk ranar da ka fito fili ka gaya mata ba ni da ra'ayin auranki za ta daina turo maka kai kuma ba ka so ta daina kana so ta turo ka karanta domin ta motsa maka sha'awa ko?  Ba ka ji kunya ba don girman Allah. Wataran fa sai dai ka ga ta d'auki hoton wani sashi na jikinta ta turo maka tunda baka tsawatar mata ba ka yi shiru hakan ya nuna mata cewa ta cigaba kana so tunda yar iska ce ita wallahi tallahi ka yi bala'in bani mamaki."
Ya yi shiru jikinsa a mace ya kar'bi wayar yana dubawa messages din da ta tutturo. Ya jima yana karantawa daya bayan d'aya kafin ya dube ni yana fad'in." Bai zama lallai ki yarda da abinda zan fadi ba. Amma ki sani cewa ban ta'ba tsayuwa na duba messenges dinta ba balle na fahimci abinda yake a rubuce. Wannan stickers din kuma idan kin lura wasu sun bud'e da kansu wasu kuma ba su bude ba, ba ni da lokacin wannan sakarcin nata kuma ban san da cewa bata da hankali ba sai yanzu."
Na jima ina kallonsa da ko'karin gazgata maganarsa za ta iya kasancewa gaskiya ne abinda yake fad'i tunda wasu sticks din ni na bud'e su da hannuna Rubutu da karantawa abu ne da dama can yake bashi wahala k'aramar magana idan zai yi ya fi gane ya kira waya zaman sa ma a online babban jidali ne domin da ya hau baya mini goma cikakku yake sauka sai wata goben Kuma idan kuma ka gan shi a online tabbas akwai muhimmin abu.
Na ce." Ka dai ji tsoron Allah wallahi tallahi kuma ka suturta furfurarka ka haihu mata gasunan a gabanka duk abinda za ka yi ka tuna Allah Ya na ji yana kuma yana kallonka sannan kaima kana da zuria.
Ya yi bala'in shan kunu! yana fad'in." Me ki ke nufi ne Amina duk bayanin da na yi miki ba ki aminta ba, har yanzu kin kasa fahimtar abinda zan yi da wanda ba zan yi ba, bayan rantsuwa da Allah da na yi hakan bai yi miki ba

kina ganin akwai abinda na boye wanda nake aikatawa, idan har na fahimci maganarki anan kina so ki ce mini ina neman matan banza a waje?"
Na ce." Ni ban fad'i hak..... Ya katse ni ta hanyar buga gefan katifa da hannunsa na kalle shi cikin kad'uwa da mamaki yanayinsa gabad'aya ya canza. " Ya furta." Ba ki fad'a ba na yi miki k'arya kenan kuma za ki k'aryata kan ki ne, gashi kina misali akan yarana idan na 'bata na wasu ni ma za a 'bata nawa. Duk tsayin shekarun da na yi a can baya ban yi aure ba kuma ban yi zina ba sai yanzu da girmana da kuma shekaruna. Kin jima kina kausasa mini kalamai irin yadda ranki ya so, ba ki da mutunci wasu lukutan ba ki daraja ni, kuma ba kya kar'bar kuskure da ajizancina. Idan ina neman mata tsayin zamana dake duk takatsantsan dina watarana za ki gane hakan me yasa ba ki da kirki ne Amina."
Cikin tashin hankali nake kallonsa ganin yadda gabad'aya ya rikice har zufa yake yi kamar ba wanka ya yi yanzu ba fitowarsa ya kashe Ac din dake d'akin.
A rikici da b'acin rai ya nuna ni da yatsa yana cigaba da cewa. " Idan har zan nemi matan banza bari na gaya miki yadda nake fitacce
masu aji da tsabta zan nema irina  ba irinsu wannan matar ba da kuka matsanta mini a kanta ba, ina so ki kara  sani ni mutum ne  mai kishi idan ba dole ba da kuma 'kaddara ba ba ni so na yi tarraya da abu wani ma ya zo ya yi, ban ta'ba sha'awar wannan harkar ba duk tarin ni'imar da Ubangiji ya yi mini, abinda kuma ki ke fata ya kasance kan abinda muka haifa ba zai faru ba tunda ban yi ba Allah ba zai jarrabe ni ba."
Daga haka ya tashi tare da d'aukar hularsa ya sanya ya nufi ma'adanarsa da yake ajiye gilasansa ya zari daya ya sanya ya kwashi wayoyinsa ya kama hanyar fita babu annuri a fuskarsa.
Shiru na yi bayan fitarsa na gaza tab'uka komai saboda mamaki yadda ya burkice. Can k'asan zuciyata na ce mini tabarmar kunya ce fa yake nad'eta da hauka domin ya k'waci kansa duk hargagin banza ne. Na yi shiru sosai ina sake nazarin maganganun da ya furta. Tabbas kamar yadda ya fad'i mutum ne mai tsananin kishi. Tun bayan haduwarmu ta farko a ofis dinsa da ya zo mini da maganar banza bisa wata hujja tasa to tun daga lokacin ban sake ganin wani abu na sakarci da b'acin suna daga wajensa ba. Yana da ibada daidai gwargwado sadaka kyauta ciyarwa kulawa da marayu wasa da dariya da iya mu'amula.
Da'biarsa mummunan da na sani gaba da k'ullaci kuma cikin ikon Allah da zama ya yi zama a tsakaninmu ya rage. Ban ta'ba cin karo da wasu alamu da za su nuna shi din manemin mata ba ne gaskiya idan na ce na gani na yi masa sharri tunda a yanayin yadda yake mu'amulantarta a shimfida ma wannan ya isa sheda da tabbatar mini da cewa bashi da lokacin bibiyar wasu matan a waje. A yanzu dai idan na fahimci abinda ya hasala shi bai wuce don na ce ya ji tsoron Allah ba saboda shima ya haifa wannan maganar itace ta tunzura masa zuciya har ya fita da b'acin rai! Mai tsanani hakan na tabbatar mini da cewa ya ji ciwon maganar sosai kuma abinda duk ya fad'a gaskiya ne yau kan an kira ni da mara mutunci mara kirki dole na bada ha'kuri Allah Ya sawwa'ke.....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*165*
Ban yi zaton fushin zai tsananta da yawa haka ba. Tunda a daran ranar da lamarin ya faru na bashi ha'kuri tare da nuna masa na yi kuskure sai ya dinga ciccijewa haka muka kwana bai ce mini komai ba da gari ya waye na gaishe shi ya amsa da k'yar. Still da ya fita ya dawo da yamma nan ma na sake bashi ha'kurin bai huce ba. Abinci ya'ki ci na dare da jiyan da yau a gidan Hauwa yake zuwa ya ci. Ganin kamar kwantar da kan da nake yi ina bashi ha'kuri yana Kara masa kuzari da karsashin yi mini wulakanci sai kawai na 'kyale shi Hauwa ta kar'bi girki ya je ya yi kwanaki biyu ya dawo mini babu fuska har yanzu zai amshi gaisuwata amma akan dole ko na hau saman na same shi sai ya tsiri aiki a loptop ko ya kira yara su yi wasa. Abin ya fara ba ni dariya da mamaki. Na yarda na yi kuskure kuma ban kyauta ba na nemi afuwa sai a yafe mini ai a cigaba da cud'a rayuwar amma sai ya samu hanyar hura hanci da d'aga kai ganin ina binsa da kwantar da kaina dama dabi'arsa ce haka idan ana ba shi ha'kuri sai ya kara hawa ba zai sauko ba.
Gaisuwar ma sai na daina na zura masa ido ko ni nake da girki ba ni hawa saman abinci kuma tunda ya daina ci na daina kai masa.
Muka cigaba da tafiya haka tsayin sati biyu babu wani sukuni a tattare da shi domin alamu sun nuna ya fara gajiya yana ta kame-kame.
Da daddare na yi shirin kwanciya tsaf ina zaune Ina bawa Hasan nono shi bai yi baccin ba tukkuna ya turo kofar d'akin ya shigo cikin jallabiya k'amshin turaransa ya mamaye d'akin gabad'aya ya had'u da wanda na yi amfani da shi.
Na d'aga kaina na kalle shi muka had'a ido sai na yi 'kasa da kaina dama ni ban zafafa ba ai ya nemi wuri ya zauna a gefena babu yabo babu fallasa na sake kallonsa muka had'a ido a hankali na ce." Sannu."
Bai amsa ba ya d'ora hannunsa saman goshin yaron yana fad'in." Minal ta ce mini ba shi da lafiya?"
Na ce." Lafiyarsu lau fa ta ji yana dan tari d'azu shine take tambayata wai bashi da lafiya na ce mata kalau yake."
Ya kar'be shi daga hannuna yana fad'in." Tari ba ciwo ba ne Amina."
A takaice na ce." Ciwo ne amma ba irin wanda nake tunani ba. Nono yake sha sai ya d'an 'kware shine bashi da lafiya in ji ta."
Ya d'an yi shiru na wani lokaci kafin ya furta." Jiya Hauwa a asibiti ta kwana bata da lafiya!"
Na dube shi da sauri " Bata da lafiya?"

Ya gyad'a kansa ya ce." Ciwon ciki ta yi sosai daga karshe dai cikin nata ne ya fice! amma alhamdulillahi ta samu sau'ki tana gida."
A d'an sanyaye na ce." Ban sani ba wallahi, kai za ka gaya mini kuma kana jin haushina."
Ya ce." Gashi yanzu na gaya miki ai."
"Allah Ya bata lafiya." Na fad'a cikin jin wani yanayi ta ba ni tausayi wallahi domin ta kallafawa ranta cikin Allah bai yi zai zo duniya ba.
Shiru na tsayin lokaci kafin ya kwantar da yaron kusa da d'an uwansa. Ya gyara kwanciya a gadon. Na dube shi yana lumshe idonsa yau anan za a kwana kenan.
Bai ji ma da kwanciya ba ni ma na kwanta a gefensa tunda dama na yi shirin kwanciyar.
Ya bude idonsa yana kallona ni ma shi din nake kallo wai akace labarin zuciya a tambayi fuska duk kame-kamen da yake yi na gane. Ya d'an janyo ni kusa da shi can k'asa na ji maganarsa yana fad'in.'' Kin yi mini abubuwa da yawa na kyautatawa da kuma alheri ba kuma zan mance ba."
Ya nisa kafin ya cigaba da cewa." Wad'annan maganganun da ki ka yi a kaina sun yi mini zafi k'warai da gaske ina so wannan ya zama na farko ya kuma zama na k'arshe kada ki kara dangantani da haramci da abinda Allah ya la'anta. Ki san irin maganar da za ki dinga gaya mini wadda ta dace da wadda ke kanki kin san kuskurene. Ba ni da nufin auran Nabila a cikin raina na fad'a muku maganar ba d'aya ba sau biyu ba wallahi ba ta ta'ba ba ni sha'awa ba balle har na yi tunanin yin zina da ita ba zan boye miki ba har yanzu idan na kalleki na tuna abinda ki ka jingina mini raina yana b'aci wallahi."
A hankali na ce." In sha Allahu, Allah Ya ba ka ha'kuri."
Ya sauke ajiyar zuciya tare da d'an matse ni a jikinsa shikkenan daga lokacin kuma sai komai ya sauya..
Wai aka ce fad'an masoya hutu ne.
Da gari ya waye duk da bai sake yi mini maganar Hauwa ba amma ni da ita na kwana a raina domin yadda ya ke fadi ta sha wahala sosai kafin ma cikin ya fita tunda har sai da aka kwanta a asibiti kwana da yini.
Sai da yamma na shirya lokacin yara duk suna makaranta muka tafi da Mairo saboda yaran ita goya Hasan na ri'ke Usaini a kafadata.
Mai aikinta Ladidi tana ta goge -goge ita kadai a falon muka gaisa ta ce mana tana ciki a akwance na ce ta shiga ta gaya mata.
Minti uku ta fito tana sanar da mu cewa gata nan. Ta nufi kicin da sauri.
Mun kai kusan minti goma sha biyar a zaune kafin ta fito daga cikin bedroom dinta ta d'ashe sosai kamar wata mara jini duk sanda take da ciki haka take irin wannan mugun hasken fau! yanzu abin ya hadu da d'aita domin da alamu cikin nan a k'alla zai yi wata hudu zuwa biyar ta sanya rai.
Ta ba ni tausayi sosai ta zauna kamar mara laka a jiki babu kuzari da karsashin tana fad'in." Ashe kune in banda shiririta irin na Ladidi ai da sai ta gaya mini cewa ke ce."
Na ce." Ba sai ta san ni ba Hauwa."

Ta d'an yi murmushi kafin ta ce." E hakane bata ta'ba ganinki ba sai dai labarinki wurin yara."
Na gyad'a kaina ina sake nazarinta a nutse na ce. Ya jikin Ubangiji Allah Ya baki lafiya Allah ya mayar da abinda aka rasa."
Ta amsa da "Amin suma Amin na gode sosai."
Mairo ta gaisheta da jiki ta amsa tana kallon Hasan dake goye a bayanta sai kuma ta dube ni tana yar dariya ta ce." Sun k'ara wayo sosai yaran nan Amina."
Na ce." Sosai ni ma na ga girmansu wata uku muke yanzu."
Ta ce." Hakane kam."
Ta yi shiru tana lumshe Idonta na ce." Za mu tafi Hauwa Allah Ya kara afuwa."
Ta bude idonta tana kallona a daidai lokacin dana tashi tsaye ta ce." Na gode sosai."
Muka kama hanyar fita ni da Mairo. Na ji tausayinta gaskiya abin babu dadi.
Da ya dawo ya ji labarin na shiga dubata ya yi murna sosai yana fad'in da haka kuke yi tun farko ai da na ji dad'i Amina."
Kwana biyu ba sai jikin nata ya kara rikicwa ba ranar girkina ne da daddare wajan sha biyu da wani abu lokacin muna shirin kwanciya ta kira waya cikin mayuwacin hali ciwon kai matsananci jini kuma ya tsinke mata.
Tare da ni da shi muka nufi gidan a ki'dime lokacin ma ta fice daga hayyacinta mai'aikinta na ta ihu jini ya bata jikinta da bedsheet din da take kwance a kai.
Muka gigice ni da shi domin dai kamar babu rai a jikinta.
Jikina na tairairayota ina kiran sunanta ko'ina a sake. Ya fita da sauri yana kiran waya.
Kuka na fara yi ganin yadda take wata irin jijjiga ina kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un! taune lebanta take yi hakan ya tabbatar mini da cewa jijjiga take yi domin duk rik'on da muka yi mata ni da Ladidi sai da ta fi karfinmu.
Ya shigo da kansa ya ciccibeta tunda dama ba wani nauyi ne da ita ba. Na ce ya bari tukkuna a kintsa mata jiki domin a 'bace take da kaina na gyara mara jikinta cikin wannan yanayin ya fita da ita rai a hannun Allah muka bi bayansa Sukairaju ya kunna mota. Ya ce da mai'akin ta koma gidan tare muka tafi asibiti a daran emagency da yake sananne ne a take manyan likitoci suka rufu a kanta.
Muka kwana a zaune da jiran saurare sai gefin asubahi tukkuna wani likita ya fito ya ba mu tabbacin cewa sun shawo kan matsalar da ikon Allah yanzu haka har an daura mata jini jini tana da buk'atarsa.
A lokacin ne hankalinmu ya kwanta ya ce Sukairaju ya mayar da ni gida saboda yara ni ma hankalina yana kansu amma duk da haka sai nake ganin kamar ina matsawa za a ce mini babu ita.
Babu wanda na gayawa halin da ake ciki har yaran gabad'aya. Sai Baba Tabawa itace ta sani tunda a hannunta na bar su hassan. Har yaran suka tafi skull ba ni da kuzari na kira shi ya fi sau biyar a safiyar yana gaya mini ta ji sau'ki bacci ma take yi shima gashinan zai dawo domin ya yi wanka.
Da 'kyar na iya yin karin kummalo na zauna a d'akina sukuku don yaran ma dana lura za su dame ni da koke-koke na ce da Mairo ta zo ta d'auke su. Na

zauna ina ta tunanin rayuwa yadda Allah ya jirkitar da hallitar Hauwa jiya kadai shine abinda ya tsaya mini a raina. Muna ta hauka rai da rayuwa da jin dad'i duka ba a hannunmu yake ba. Hawaye suka ziraro mini kaina ya d'auki caji da tunani da zullumi tare da nadama da addu'ar kada Allah Ya d'auki rayuwarta a yanzu ina so mu yi nisan kwana tare mu raini yaranmu.
Wajan tara da arba'in ya shigo. Ganinsa cikin nutsuwa ya sanya ni sauke ajiyar zuciya ba mu yi wata magana cikakkiya ba har sai da ya yi wanka da breakfast tukkuna na fara tambayarsa jikin nata ya ce.''Ta ji sau'ki alhamdulillahi jininta ya hau sosai sanadin damuwar da ta tsanantawa kanta ba ta bacci ga ciwon kai mai tsanani abinda ya fita Allah ya yi ba rayayye ba ne na gaya mata tun ranar da lamarin ya faru tana ta kuka da tsananta damuwa idan da rabo ai za a samu
wani."
Na ce." Sosai kuwa in sha Allahu za a samu damuwar ai bata da amfani tunda itace ta haddasa mata shiga wannan yanayin.
Ya ce." Abinda nake so ta gane kenan, za mu cigaba da ro'kon Allah Ya kawo mana masu albarka."
Na ce." In sha Allahu rabbi."
A takaice dai sai da ta yi kwana bakwai a kwance a asibiti tukkuna ta warware sosai kullum sai na je na dubata ban taba d'auke rana d'aya ba. Inna Uwani ta zo kwana biyu da suka wuce babu yabo babu fallasa tsakanina da ita Muna gaisawa sai dai babu wani sakin jiki da juna. Yara ma sun je sun dubata sau d'aya masu aikina ma haka.
ranar da suka bata sallama da wuri na je ban kuma jima ba na dawo gida.
Sai dai ganinsa tsaye a bakin gate din gidan Hajiya Maryam shi da wasu 'kwarori guda biyu da jami'an tsaro abin ya ba ni mamaki da d'an tsaro duk da yana da masu tsaro a kewaye da shi da gidajensa amma ganin shi da wad'annan da kuma 'kwarorin sai abin ya ba ni tsoro yanayin da suke ciki ya nuna kamar akwai matsala.
Na hangi fitowar Nusaiba da Adam daga cikin gidan fuskokinsu dai babu nisha'di. Sukairaju ya shige da motar ciki bayan an bud'e gate din hankalina ya kasa kwanciya ko da na shiga ciki gidan kai tsaye d'akina na zarce ban bari sun san na dawo ba. Allah dai yasa lafiya.

Na kudi ne don Allah kada ki karanta ba tare da kin biyani hakkina ba

Minti goma sha biyar a tsakani ya shigo ya biyo ni har cikin d'akina yana ta fad'a. Ashe wad'an-nan k'warorin abokanan business din Nabila ne mazauna jahar lafia sun kashe wani d'an uwansu suka gudu ita kuma tsautsayi da azal ya sanya da suka kira ta a waya suka ce sun shigo Abuja za su zo su yi magana akan wata harka ta alheri ta gayyace su zuwa gida a jiya da daddare a yadda take fad'a cewa ba ta ta'ba tunanin za su kwana ba balle har ta ba su mafaka domin da suka gama tattaunawa ta yi ta yi da su su tafi suka 'ki suka wayi gari a zaune. A jiyan da daddare akwai wanda jama'an tsoro suka sanya domin yi musu bincike da yake Ubangiji Allah baya bacci kuma cikin

gaggawa yake tona asirin hakkin rai mutumin ya gaya musu ga inda mutanan suka fake nan. Abinda ya tsananta domin har itama Nabilan na cikin tasku saboda bincike dole ya bi ta kanta tunda sun ce har da ita da kuma sanya hannunta alhalin k'arya suke yi. Tana cikin gidan taki fitowa sai da ta ji duka tukkuna yanzu sun tasa keyarsu gabad'aya can garin nasarawa lafi'a. Allah Ya tsare mana imaninmu.
Da ya gama gaya mini ya shige toilet domin yin wanka ya barni da tu'ajibi da mamaki wai 'ya mace ta'ki kama kanta saboda masifar son abin duniya. Ba a hana mace yin kasuwanci ba amma a yi mai tsafta da aji da kuma ilimi. Gashi dai sun dilmiyata cikin case dinsu bayan su kansu sun san bata da hannu a ciki. Wannan shine
abinda ya yi rayuwar Hadiza illa kenan.
Ya fito daga toilet din yana cigaba da fad'a tare da jaddada mini cewa ba zai ta'ba sanya hannunsa a cas din ba tunda ba shi ya aiketa ba hanya yake nema dama tunda rayuwar da ta d'aukarwar kanta kenan shikkenan babu ruwansa abinda dama ya sanya shi barin ta a gidan a zaune saboda yaran sun buk'aci hakan ne shikkenan gida za a rufe idan Salim ya tashi aure yana da ra'ayin gyara wani bangare daga ciki sai ya zauna da iyalinsa tunda sun ce ba sa so a sayar kuma ba sa so zuba y'an haya. Adamu zai ba shi za'bi zaman kano gidan Hajiya Ayya wurin kakarsa ko kuma zama anan wurinmu duk wanda ya zab'a daidai ne.
Ko da ya tambaye shi kuwa yaro ya ce kano gidan Hajiya Ayya ko gidan Hajja. Ya ce gidan Hajja ya fad'i hakane saboda Yusi ya ce zai yi waya da kakar tasu domin sanar mata da halin da ake ciki.
Lamarin nan na jima yana ba ni mamaki da tsoro duniya ta lalace yanzu mutum akan abinsa dukiyarsa sai a halaka shi tunda bincike ya tabbatar da cewa akan kudinsa ne suka kashe shi gashi dai tare suke su uku kuma kowa ya sansu a tare amma an wayi gari sun kashe shi. Abin tausayi da jimantawa ita Nabilan da Allah ne kadai zai fitar da ita. Shiyasa ko abota za ka yi kasan da irin wad'anda za ka yi.
Saurin yarda da sakin jiki ga mutumin da baka sani ba sai ya janyowa rayuwarka barazana. Allah ya k'ubtar da ita tunda babu gata ta ko'ina ba uwa babu uba, yan kudin nata da take nema ba su isa su fitar da ita daga wannan masifa ba ga yaranta biyu duk maza sun zama yan samari wata'kila ganin sakarcin da take yi ne ya sanya ubansu kar'be su suna can jos din tunda a can ne ta yi auran kafin ta fito.

Yau kwanaki biyar kenan da fitowar Hauwa daga asibiti Hajja ta zo dubata a gidana ta sauka sai da ci abinci tukkuna ta huta sannan muka nufi gidan tare tunda ni ma tun bayan an sallamota daga asibitin ban sake duba ta ba.Kafin mu isa gidan Hajja na jaddada mini jikin Gwaggo babu dad'i kwanakin nan itama tana fama domin ta kwanta a asibiti na kwana uku kafin a sallamota ban ji dad'i ba kuwa ba a gaya mini ba Hamusu bai sanar da ni ba haka zalika ma Yusi. Raina ya baci sosai amma ban nuna mata ba tunda babu halin kalubalantarta. Duk da saura kwanaki mu shiga ramadan hakan ba zai hana ni shirin zuwa dubata ba jikinta ba ta d'an jima a tsaitsaye tana ciwo ashe

har da kwanciya a asibiti gashi masu aiki na shirin tafiya umara kamar yadda maigidan ya yi musu alkawari a farkon farkon watan azimi.....✍

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*166*

Sosai na yi dana sanin bin Hajja zuwa gidan Hauwa da ina da masaniyar abin da zai faru. Wannan shine dalilin da ya sa da yawa wasu daga cikin mutane ba su son yin auran zumunci a tsakanin yaransu koda kuwa akwai soyayya mai karfi a tsakanin yaran akan samu suka da kalubale daga wurin dangi kowa na fad'in albarkacin bakinsa akan zumuntar da za a had'a ta aure wadda ake da burin ta d'ore ta ginu ta kuma kara karfin zumunci tare da albarkar haihuwar yara.

Mafiakasari shi auran zumuncin bai fiye yin armashi ba wani tun daga farkon k'ulla shi ake fara cin karo da rigingimu mabambamta wanda ka iya janyo rabuwar kai da tashin hankali tare da zama a teburin sulhu idan ma ba akai zuciya nesa ba har hukuma kan iya shiga domin kawo sasasanci dalili daga kowane bangare yana ganin ba a yi masa daidai ba.

Wannan tashin hankalin ya sanya da yawa iyaye suka gwammace su aurawa na waje yaransu domin samun nutsuwa da kwanciyar hankali duk da cewa rikicin aure da matsaltsalunsa abu ne da ya zama ruwan dare ko da babu dangantaka a tsakani a duniya a ka hadu har aka kulla auratayya matsala na faruwa iri-iri tunda dama kafatanin auran ha'kuri ne jin dad'insa kad'an ne. Amma dai da sauki akan ace abu biyu ne suka hadu waje daya dangantaka ta jini zumunta mai karfi kuma da dangantaka ta aure sai abin ya zama wani iri iyaye su shiga idan an kai magaryar tu'kewa lamarin ya yi tsamari a tsakanin jini d'aya a samu rabuwar kai da zargin juna daga kowane b'angare duk domin kiwatar kai bisa zargin zalintar juna.

Abinda ya faru kenan da shigarmu gidan Hauwa ni Hajja gaisuwa kawai ta ratsa a tsakani Inna Uwani ta dinga kuka tamkar wadda ta yi rashin jinji nan abu tana fad'in idan abin nan bai zai yiwu ba a rabu tunda  akwai maslaha a sha'anin aure Ubangiji da ya umarci a yi shi ya hallata rabuwa (saki) domin samun zaman lafiya da kwanciyar hankali tana kuka tuk'uru tare da jadadda Hajja Hauwa ce kadai ta rage mata a duniya a yanzu tana ji tana gani kuwa ba za ta bari ta yi asararta ba saboda bak'incin da kishiya take gumamata miji ma ya guma mata nasa.

Hajja dai shiru kawai ta yi jikinta a mace tana kallonta ita na kuka Hauwan ma na kuka irin mai ciwon nan.. ganin haka ya sanya na yun'kura na tashi jikina a sab'ule gwiwata duk ta sage saboda ganin wannan lamari bai yi mini dadi ko kad'an ba amma Allah ne shahidi idan har ina cutar Hauwa a zamantakewa to ina ro'kon Allah Ya saka mata.

Na ji maganarta tana fad'in." Dole ki tafi ki tafi Amina ke ma kin san abubuwan da kuke yi wa yarinyar nan ba ku kyautawa idan har tana da hakki a kan ki da shi mijin naku ta bar ku da Allah."
Tana kuka ita Hauwan  ta ce." Ban ce miki  Amina ta yi mini wani abu ba inna, ni kawai na gaji da zama da mutumin da bai san raunina ba bai kuma yarda ya haihu da ni ba sannan bai san ya rarrasheni ya tausaya mini idan ina cikin b'akinciki ba. Wallahi da gaske nake Hajja na gaji yara Allah Ya raya su tunda dama ai ba hannuna suke ba."
Hajja ta dube ni a sanyaye ta ce." Zauna yadda muka zo tare haka za mu tafi tare ai ke ma ba bare ba ce."
Na koma na zauna din
Kamar yadda ta umarta.
Ta dube yar uwarta cikin nutsuwa ta furta." Tunda kun yanke shawara kan cewa rabuwar kuke buk'ata abu ne mai sau'ki ai Uwani dalili ni kaina lamarin nan ya ishe ni wallahi ba zan tantance wanene mai gaskiya ba a tsakaninsu Tajo ne ko ita Hauwa. Amina kuwa ku daina sanyata a ciki babu abinda ya shafeta ban fad'i haka don ina goyon bayanta ba. Ita da Hauwa duk daya suke bambanci kawai ita tana bin umarnina tana kuma yi mini biyayya bisa duk abinda na umarceta tana son abinda nake so wata'kila ba ku san da cewa asalin auranta da mijinta umarni ne daga gare ni ba gani daya rana d'aya da ni da ita mun roki Allah kuma ya amsa mana bata san ni ba, na nemi alfarma ta yi mini a lokacin da mata da yawa suka guji auransa saboda ceton ransu ita tace ta ji ta gani duk da tana da labarin abinda ya faru da shi a baya. Wannan shine abinda ya dasa mini kaunarta cikin zuciyata kuma ban fifita ta a kan ki ba Hauwa na dai gaya miki bambancinku amma tunda kun yanke shawara a tsakaninku zan same shi domin gaya masa uzurinku sannan kuma ina so nasan abinda yake yi miki na take hakki ai dole ne shima a nuna masa kuskuransa tunda ni uwarsa ce kuma har yanzu yaro ne a wurina dole ya bi abinda nake so."

Littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba

Cikin jan hancin da kame-kame ta fara magana." Abubuwan da yake mini ba za su lissafu ba Hajja dole a cikin aure nasan ana cin karo da matsaltsalu da yawa kuma dole a yi hakuri, amma ni tunda na faru a tare dashi ban ji dad'i irin yadda nake so ba duk wanda ya ba'kunce mu yasan zaman ha'kuri nake yi ya gaya mini ya kuma nuna a zahiri zama yake yi dani saboda yaran da muka haifa da kuma zumuci, duk haihuwar data ratsa tsakaninmu tsananin rabo ne yakan jima bai kwanta da ni a shimfida daya ba, ni zan ta bin sa domin neman hakkina wallahi bai ta'ba yi don dad'in ransa ba. Ya karkata b'angare d'aya ya fifitata fiye da ni ya k'aunaci yaranta Y
yana biya mata dukkanin buk'atunta  Hajja ya zan yi da rayuwata na samu ciki ya zube ya nuna bai damu ba alhalin da kyar na same shi tunda ba kwanciya muke a gado daya ba ya cigaba da abinda yake gabansa ba shi da damuwa tunda ya nuna ga da wadda ya fi buk'atar haihuwa da ita." Ta ja

hanci hawaye na silalowa a saman kuncinta ta cigaba da cewa." Ni na gaya muku ba ta yi mini komai lefi nasa ne tunda ya kasa daidaita tsakani na da ita ya fifitata ni kuma yana nuna mini kamar akan dole yake zaune da ni."
Hajja ta tsira mata ido kawai tana kallonta. Ni kuwa na shiga nazarin maganganunta. Abinda ya kara tashin hankalinta zubewar cikinta tunda kowa ya san yadda ta jarbatu da haihuwa idan har gaskiya ne abinda ta fad'i a kansa to
bai kyauta ba wata'kila ita tana d'aya daga cikin jerin mata masu buk'ata shi kuma ba a jarrabe shi da ita ba. Ga ciki ta samu tana murna tunda ta fad'i dama ba ta so na fita yawan yara a gidan to sai kuma ya zube shi mai cikin bai nuna damuwarsa ba, ga ni kuma ina haihuwar bibbiyu shine babban tashin hankalinta abubuwa da yawa suka taru a zuciyarta."
Na ji Hajja tana fad'in. " Haihuwa ta Allah ce Hauwa itama Amina bibbiyun da take haifa ba ita ta bawa kanta ba rabo ne, kuma akwai gadonta a jininta. Amma kuma idan har da gaske ne abinda ki ka fada lallai akwai buk'atar zama a tsakani domin ai ke ba baiwa ba ce mutum ce me zai sanya shi ya dinga take hakkinki a shimfida wannan cutarwa ne ki yi hakuri ki barwa Allah ikonsa kin ji ko, wad'annan da ki ka haifa uku ki yi ta yi musu addu'a Allah Ya raya miki su sai ki ga sun tara miki garke guda. Wani ma yana can Allah bai ta'ba bashi haihuwar ba kuma haka zai koma ga mahallicinsa. Lallai zan yi masa magana idan har ba zai gyara ba to sai ya baki takarda ba dalili ba ne wannan Allah cewa ya yi idan har ba za a yi adalci a tsakanin mata biyu uku hud'u ba to kada a yi domin gujewa sa'bawa Ubangiji."
Inna Uwani ta goge fuskarta tana fad'in.'' Ni kaina abin nan ya ishe ni wallahi na gaji da bata ha'kuri da danneta akan ta zauna. Yanzu ga shi ta hadu da hawan jini saboda tarin damuwa."
Hajja ta ce.'' Uwani na ce miki abin zai zo da sauki ai, shi wanda yake da alhakin sakin a yau zan zauna da shi domin mu samu matsaya kada wannan ya dame ki."
Ta yi sakato da baki tana karyar da kai gwanin ban tausayi.
Ta yun'kura ta tashi a hankali tana gyara yafan mayafinta ta  dube ni tana fad'in." Tashi mu tafi." Na tashi da sauri domin dama kamar akan 'kaya nake a zaune a wurin.
Ta dubi inna Uwani tana Fadin." Idan an yi Isha'i sai ki shigo domin jin ina aka kwana."
Da sauri ta ce." To shikkenan." Ta sake duban Hauwa a karon da ba zai lissafu ba ta ce." Ke Kuma ki kara hakuri kin san dai illar yawan tunani da damuwa ko tunda ga abinda ya haifar miki don haka ki cire duk wani zullumi da tunani da ba'kin kishi a ranki Hakan shi zai sanya ki samu zaman lafiya."
Daga haka sai ta kama hanyar fita na bi bayanta cikin rashin karsashi.
Muka isa gidana babu wanda ya yi magana. ban ta'ba ganin tsananin bacin rai a fuskarta ba sai yau damuwa gabad'aya duk ta dabaibayeta ga tarin shekaru don ma da kula sosai amma matsalar nan kadai ka iya tayar mata da ciwonta. Na rasa da wane kalami zan rarrasheta domin kwantar mata da hankali saboda gabad'aya yanayinta ya canza da bakincikin abinda ya faru.

Na gyara mata fillo a masaukinta ta kwanta tare da mike kafarta na fita daga d'akin cikin mutuwar jiki da tunanin mugun kishin Hauwa a kaina shi zai halaka mata rayuwa kamar yadda hajjan ta fad'a domin kuwa duk mai hankali yasan tsananin kishi ne yake damunta da ganin k'yashi.

Ban san yadda ta kaya a tsakaninsu ba domin tunda na shiga d'akina ban fito falo ba ya dai kira ni a waya da ya dawo to nasan dole za su zauna zaman tattaunawa yara ma sai Mairo ce ta kawo mini su tunda wurin baba Tabawa na bar su.
Sai can wajan goma da arba'in na dare ya kira ni a waya lokacin nasan sun tashi.
Na leka domin dubata tana saman dadduma a zaune da cazbaha a hannunta ganin haka ya sanya na ja mata kofar kai tsaye saman nasa na nufa zuciyata na dokawa haka kawai rashin hakurinsu na nema ya d'agawa tsohuwa hankali.
Ya fito daga wanka yana sanya kaya a jikinsa kafin na zauna ya ce na kawo masa abinci ban ce komai ba na sake sauka kasan da zummar bin umarinsa.

Abinci ya ci ya koshi sosai ina kallonsa babu wata damuwa mai gigitarwa a tattare da shi ya kammala ya goge bakinsa da tissue ya ja gefe na sauka da tiran abincin kasa na dawo na same shi jingine jikin gado yana duba wayarsa. Zamana bai sanya ya dube ni ba. Abin nema yake yi ya shafe ni kenan tunda magana ma ta gagare shi. Ban nemi lallai sai na ji halin da ake ciki ba tunda bai shafe ni ba idan shi ya gaya mini zan saurare shi ba ni da wata shawara da zan ba shi akai duk abinda ya yanke a tsakaninsu daidai ne.
Na daure zuciyata na kalle shi a nutse na ce." Ina tsammani tare za mu tafi da Hajja zuwa Kano Gwaggo fa jikinta babu dad'i tun lokacin haihuwar yaran nan take ta fama wallahi ya kamata na je dubata."
Ya yi shiru bai ce komai ba. Sai da na sake maimaita maganar tukkuna ya dube ni yana fadin." Don Allah kada ki k'ara mini wani b'acin ran Amina a bar ni cikin wanda nake a yanzu."
Na ce." A a ban gane kada na bata maka rai ba, zuwa duba jikin Gwaggo shine abin b'acin rai kuma?"
Ya shiru bai tanka mini ba."
Na ce." Ka dai duba don Allah babu rashin dacewa fa kuma ciwo ake dubawa."
Ya ce." To zan duba idan zai yiwu ."
Na ji wani takaici ya yun'kuro mini amma sai na danne na yi masa uzuri saboda yanayin da yake ciki na damuwa.
Haka muka wayi gari zuciyoyi babu dad'i da safe kafin na sauka kasa ta kira shi a waya aikuwa ya fashe tunda dama ya kumbura sumtum! jira yake yi a zungure shi ita in banda abinta tasan abinda ta yi kuma ai sai ta ja gefe ta yi zaman saurare. Fadi yake yi "Ban yi niyyar sakinki ba Hauwa ku kaini 'kara kotu mara mutunci masu mance alheri. Ni za ki yi wa wannan iskancin duk abinda nake yi miki ba ki ga ni ba sai kin had'a ni da uwata tuntuni na gaya muku ba ni son abinda zai d'agawa mahaifiyata hankali da girmana ku dinga

yi mini terere babu wadda za ta rufa mini asiri ba ni da sirri a gidana. Kin cire kunya kin gaya mata karya da gaskiya ba ni baki hakkinki ni za ki yi wa sharri Hauwa wato duk ko'karin da nake yi miki ba ki gani ko? Ga ni ki ke yi yawan kwanciyar aure shi yake kawo haihuwa kina ganin daga 'bangarena ne haihuwar biyu da Amina take yi ba baiwa ba ce da rabo daga wurin Allah. Shikkenan kin buk'aci rabuwa ni kuma ba zan yi rabuwar a lokacin da kuka buk'ata ba.
Na ji cikin rawar murya tana fad'in." Ni wallahi ban ce mu rabu ba, cewa na yi ka gyara kuskuranka ni ma na gyara kuskurena mu zauna lafiya ai kowa ya sani ka fi buk'atar haihuwa da Amina kuma soyayyar da kake yi wa yaranta ya fi wanda kake yi mini da abinda na haifa."
Na cika da mamaki kwarai jin yadda take fad'in ita ba tace su rabu ba kenan k'aryata Hajja za ta yi bayan su suka fad'i haka.
Ya ce." Kina nufin Hajja ta fad'i hakan ne kawai domin ta ji dadin bakinta kenan, so ki ke na lalace a gadonki na dingi jima'i dake saboda ki tara yara kin d'auka sakarai ne ni da ban san abinda nake yi ba, ko kin yi zaton ban fahimci gasar haihuwa ki ke yi da Amina ba. Duk abubuwan da kuke gudanarwa a gidan nan daga ke har ita ina sane kuma ina bibiya shiru kawai nake yi muku. Ba zan sake ki ba, kuma ba zan sake yin cikin da za ki haihun ba sai mu ga yadda za ki yi."
Ya kashe wayarsa yana huci! Na dinga kallonsa gabana na fad'uwa. Oh! ikon Allah wata ta kunno bala'i yana nema ya shafe ni Ubangiji Allah Ya sawwa'ke musu wannan masifa.
Na tashi na sauka bai ce mini komai ba ni ma ban yi masa sallama ba.
Bayan kwana biyu da kansa ya ce na shirya da safe sai mu tafi tare gabad'ayanmu zuwa kanon shima zai duba jikin Gwaggon.
Na yi godiya a takaice babu wani sakin fuska domin haushinsa nake ji ganin yadda yake nema ya jingina ni a jikin badakalarsu.
Tare muka nufi kano a washe gari wanda ya yi daidai da saura kwana biyu a d'auki azimi a ranar da daddare ni da shi muka je har gida duba Gwaggo da sauki za a ce amma dai da kyar ta gane ni. Hamusu kuwa ya sha fad'a a wajensa ganin haka ya sanya ban yi masa nawa fad'an ba tunda an had'a gabad'aya an yi masa menene amfanin abinda ya yi wai kada a d'orawa mutane nauyi wannan maganar ta yi bala'in bata mini rai.
Da sassafe a ka d'auketa a kai kaita asibitin Malam tunda dama tana file Dr Iliyas da abokanan aikinsa suka shiga bata taimakon gaggawa.
Kwana daya ya yi ya juya ya ce yana da uzuri amma da shara'din na biyo bayansa da kwana biyu na ce masa to kawai ba ni kuma tsammanin bin sa sai na yi sati gidan Hajja na zauna bangaranmu na gidan. Ban zo da mai aiki ko daya ba tunda tafiyarsu a cikin satin nan ne azimi da kwana uku ko hudu yaran kuma sun dan yi wayo ni da iyami mai aikin Hajja muke kula da su.
Da daddare ma da zan sake zuwa duba jikin Gwaggon a gida na bar su wajanta Magaji ya d'auke ni a mota zuwa asibitin Malam din.
Wani ikon Allah wai ana tunanin samun sau'ki da rangwami a wajan da aka kaita domin kula da lafiyarta sai abin ya kara rikicewa jikin ya'ki dad'i yadda

ake buk'ata Gwaggo ta kai ta kawo sai da aka sanya mata abin numfashi a hanci saboda bata iya yi da kanta.
Kuka na dinga yi a fakaice saboda tashin hankalin ganin yanayinta wani siririn hawaye na zuba ta gefan idanunta tana daga kwance a gado(tun muna yara Iya kakarmu ta wajan Uba da zata rasu ta dinga yin wannan hawayen na gefan ido aka ce mana wai na sallama da duniya ne) Gwaggo na mike a gado ana ta cuku-cuku a kanta duka rai ake yi wa wannan fafutukar amma zahiri ciwo ya ci karfinta sosai Gwaggo lokaci take jira domin tun ganin da na yi mata a gida na sare.
Babu wani kuzari muka fito daga d'akin ni da Hamusu ba mu jima muna magana ba muka yi sallama saboda dare ya yi na shiga mota Magaji ya ja muka fita daga asibitin.
Bacci mai cike da mafarkai marasa kyau na yi da asuba na tashi jiki a mace Ina zaune saman dadduma Yusi ya shigo da tsananin tashin hankali. Ganinsa a hargitse sai gabana ya fadi ya furta. Mama Allah Ya yi wa Gwaggo rasuwa. Baba Hamusu ne ya kira ni a waya yana gaya mini wai yana ta kiran wayarki a kashe d'azu da asuba ta rasu.......✍️
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*167*
Mutuwa dai itace karshe mai yanke nisha'di da walwala mai jefa zuk'ata cikin firgici a lokacin da aka yi tabbas mutane na shiga cikin hankalinsu tare da tuna yaushe tasu zata riske su kuma a wace rana ne. Mutuwa ko ta kafiri ce takan sanya tsoro da nadamar duniya to balle mutuwar mumunai daga cikin salihan bayin Allah. Ha'kika mu da muke ahalinta mun yi rashi kuma mun koka 'kwarai da gaske bisa rashin ta da muka yi amma wani abin mamaki da ikon Allah yadda ma'kota ke kuka wiwi har da yara k'ananu bisa rashinta shine abinda yake bawa kowa mamaki. Lallai Gwaggo tana d'aya daga cikin wad'anda Ubangiji Allah Ya fadi cewa tundaga  mutuwarsu ake gane cewa 'yan aljanna ne. Sosai ta samu jama'a kwarai da gaske haka zalika duk wanda zai zauna ya tashi sai ya fadi alherin da ta yi masa da jikinta ko kuma da aljihunta. Gwaggo ta samu sheda daga wurin ma'kotanta da sauran abokanan arziki duk tsayin zamanta a garin kano a kuma cikin unguwar da take aure babu abokin fad'anta tsakaninta da kowa lafiya ta rabu.
Gari yana yin haske kad'an muka tafi ni da Hajja da Yusi lokacin tuni an kawo gawar daga asibiti ma'kota mata sun cika gidanta mazansu a waje da sauran danginsu abbansu Yusi tunda dama ba wani yawa ne da su ba layin cike yake da jama'a yara da manya cikin alhini da tashin hankali.
Sai yamma tukkuna mutanan maiduguri suka iso cikinsu har da Dada kakarmu na dinga mamakin ko'karinta tunda itama bata da wani 'koshin lafiya. Ta ci kuka kuwa sosai tana fad'in ta so ta zo ta samu gawar aminiyarta ta yi mata addu'a. Anti Yagana Ya Falmata da kuma iyalin baban Saude dana

Babanmu Babagana mahaifinsu babandi tare muka yini da su da magriba Hajja ta ce na kira mata Magaji suka yi waya ta ce ya d'auko babbar motar da za ta d'auke mu gabad'aya mu tafi can gidan nata mu kwana gabad'aya har da su tunda gidan Gwaggo bashi da girman da zai d'auke mu duka. Haka kuwa aka yi bayan isha'i magaji ya zo a lokacin ne muka yi sallama da Ummansu Hadiza da Fati suka tafi tunda suma tare duk muka yini Babanmu kuwa da shi aka yi jana'izar Gwaggo shine akan gaba. Ita kuma Ummansu Saminu tana kwance bata jin dadi dalilin da ya hana ta zuwa kenan. Shi ma Usaini ya yi wa Hamusu kara sosai domin yinin ranar rufe shago aka yi duk suka zauna wajan kar'bar gaisuwa har ya kawo matarsa Hajara muka yini tare da su gabad'aya tana ta fama da d'an cikinta da ya huda zani ya fito kurcici sosai na ji dad'i  bisa wannan karar da suka yi mana.
Hajja ta sanya aka gyara musu d'aki a cikin falonta tunda da akwai dakuna hud'u duk kuma a shirye suke gyaran da Iyami ta yi kad'an ne tace su shiga su huta kafin a kawo abinci.
Muna tare da su gabad'aya don sai a lokacin ma iyalin baban Saude ke yi mini barka tunda ba su samu ikon zuwa taron sunan da muka yi ba kamar yadda ya yi mini alkawari  saboda rasuwar mahaifin Mamansu Abahuraira amaryarsa kenan. Na ce da su babu damuwa komai nufin Allah ne. Sun yi godiya sosai wai ba su zo ba amma sakon turaman atamfofi ya iske su har gida.
Ranar Kamalu muka yi bidiyo call da Kamalu ya yi wa kowa ta'aziyya tare da jajantawa cikin alhini to ya za a yi abinda kowa yake fad'i kenan lokacinta ne ya cika amma abin farincikin rahamar Allah da ake yi mata zato.
Ban yi tunanin zuwansa a ranar ba tunda duka bai fi kwanaki uku da komawarsa ba
Allah sarki sai gashi wajejan k'arfe goma sha biyu na dare har da mintina akai ya shigo gidan Hajja wata'kila tafiyar mota ce kuma bai fito da wuri ba. Ya d'an ba ni tausayi  ganin yadda rayuwarsa take gudana a tafe daga nan sai can babu wani hutu idan har an kwanta to dare shima a cikinsa sai an yi wata ibadar ta jijjiga jiki. Lokacin da ya samu kwanciya da wadataccen hutu na dole da rashin sukuni
shine lokacin da Hajiya Maryam ta shimfid'ar dashi shine ya yi kwanciya mai kamar mutuwa hutun dole ba don dad'i ba.
Muka kwana tare da shi a b'angaransa na gidan inda na sauka da zuwana. Sosai ya yi mini ta'aziya ya jajanta rasuwarsa ya kuma bayyana alherinta tare da jadadda mini ri'ke amanar da ta bashi kafin rasuwarta.
Da gari ya waye ya riga mu yin gaba domin ko cikin gidan bai shiga ba wurin su Hajja basu san ya zo ba. Ya ce duk idan sun had'u gidan rasuwar sai su gaisa.
Haka kuwa aka yi a can gabad'aya suka gaisa da su Dada ya zauna cikin jama'a ana ta kar'bar gaisuwa da shi Babanmu a gefensa da Baba Sule sai Idiris dana hange shi a gefe a zauna kusa da Baba Sule duka muka gaisa kafin mu shiga ciki nan ma ma'kotanta suna ta hidima da wasu daga cikin danginta da suka sauka jiya da daddare.

Ranar sadakar uku daga gidan Hajja aka yi abin sadaka abinci mai kyau ciki har da wainar shinkafa fanke da wainar gero da sauransu haka Magaji ya d'auki kololin abincin ya tafi ya kai gidan da sassafe.
Kafin ya dawo ya dauke mu gabad'aya zuwa gidan.
A ranar ne Sahura da Yusura suka zo mini gaisuwa da yamma kuma sai ga anti Maimuna uwargidan Alhaji Muntari tare da Salima babbar yarinyarsu goye da d'anta a baya. Na ji dadin ganinsu kuwa abubuwa da yawa suka hana ni neman inda suke a duk lokacin da na zo garin amma ina samun labarin Turmuzi a wurin Hamusu tunda ragamar kula da shi tana hannunsa har yanzu shine ma yake zuwa duba shi makaranta kamar dai yadda ya dinga d'awainiya da Kamalu.
Muka gaisa sosai cikin karamci da kulawa ta ce mini itama labarin rasuwar ta ji ta ce bari su zo tun kafin a watse tasan ina nan ban tafi ba sai su yi mini gaisuwa. Na dinga godiya kuwa ina tambayarta yara ta ce mini duk suna nan lafiya lau. salimat ta kwanto mini yaronta daga bayanta tana sinne kai Sahura na tsokanarta to abin ai ba wahala tunda dama 'kawar Yusura ce kusan sa'annin juna ne itama gata nan da d'anta daga zarar an yi auran ne sai haihuwa yanzu shiyasa wasu samarin a cikin irin abinda suke saye na angwanci suke hadawa da pampas da set din kayan sanyi domin jiran ko ta kwana.
Anti maimuna ta ce mini tana nan tana sana'arta sai abinda ma ya yi gaba domin har ta kama shago gaba da su kad'an ana sauke mata motar itace da buhuhunan gawayi tana gaya mini ita Jamila tana can harkar film take yi. Kuma sau biyu ta zo ta duba yaranta tun bayan rasuwar Babansu ta tayar da masifa a sayar da gidan a bata gadon yaranta sai da aka yi mata rubdugu jama'ar unguwa suka yi mata tara-tara kamar za su daketa sannan ta kama borin kunya yaran unguwar marasa kunya masu jini a jikina suka ce duk ranar da ta sake shigowa unguwar sai sun zane mata jiki. To tun daga lokacin ne bata sake zuwa ba wai da har ta yi barazanar shigar da kara kotu tana fad'in ba ta yarda da wajan da aka kai mata yaro ba sannan ba a nemi shawararta ba. Kuma shiru har yanzu dai ba a sake jin doriyarta ba sai dai suna ganin seriars film dinta mai suna *Gidan kashe ah* tana fitowa a magajiyar karuwai wai acan garin lakwaja ake shirya film din gidan karuwai.
Abin ya dinga ba ni mamaki da al'ajabi Jamila mai take nema a duniyar nan ita a maimakon ta zauna ta yi hakuri ta kula da yaranta marayu kamar yadda 'yar uwarta ta yi sai take ganin kamar cutar da kai da kuruciya ne gwara ta fita yawon bariki domin dai a matsayinta na ya mace mai sauran kuruciya bai kamata ta wulakanta rayuwarta irin haka ba. Salima ta d'auko wayarta daga cikin jaka ta lalobo film din tana nuna mini. Na kar'bi wayar ina dubawa Sahura na leko kanta muka cika da mamaki tana tsakiyar karuwai da sigari a hannunta suna buga karta ana shewa da tafi kuma wai film ne. Na yi sauri na mik'awa yarinyar wayarta ina kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un. Lallai idan ka ga wannan tambad'ewar akwai hakki ko kuma baki na iyaye. Ai akwai y'an film 'din masu nutsuwa da suka mayar da harkar sana'a kuma ta yi musu riga da zani wasu har da mahalli da jari amma ita hanyar da ta d'auka ba za ta yi mata kyau ba domin su kansu masu d'aukar film din suna duba dacewa

akan abinda za su d'ora mutum akai wata'kila shiga da mu'amularta ya nuna musu ga abinda tafi k'warewa a kai Ubangiji Allah Ya tsarkake mana zukatanmu.

kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Washe garin ranar da Gwaggo ta yi uku a gidanta na gaskiya muka tashi da azimin farilla na Ramadan. Kowane bawa ya samu nutsuwa da kuma kad'aita kansa ga mahallici domin samu rabauta da dacewa.
Ranar sadakar bakwai addu'a kawai aka yi mata ba a zauna ba tunda dama azimi ake yi Yallabai din yana nan bai tafi ba tukkuna shi da mahaifiyarsa suna ta fitar da abinci buhu buhu da abin masarufi domin sadaka da aka sha ruwa aka fita da d'anye hadiya ga marigiyar kamar yadda na ji Hajjan tana fad'in.
goma ga azimi suna ta wannan aikin harabar gidan Hajja cika take yi da mutane har da mata abin dai gwanin ban tausayi daga waje ma jama'a ne cike buhun shinkafa ce da kudi dubu goma ga mai rabo ban san iya adadin mota nawa ya sauke ba bayarwa ake yi jama'a na k'aruwa har sai da azimi ya raba tukkuna abin ya yi sau'ki. Lokacin kwanan su baba Tabawa tara da a kasa mai tsarki tunda hud'u ga azimi suka tafi a yadda yake gaya mini yaran suna can gidan Hauwa duk da har yanzu jikinta bai dawo daidai ba akwai mai aikinta Ladidi da kuma Inna Uwani ba ta tafi ba wai sai bayan sallah. A lokacin ne na ji hankalina ya yi gidan gabad'aya saboda ban yarda da zaman yarana a gidan Hauwa ba. Na fara yi masa maganar tafiya ya ce sai ashirin ga wata yana lissafin zakka ne sai ya kammala.
Babanmu ya kira ni a waya yana ta godiya wai an kai musu abinci har buhu biyar da taliya da sukari har da gero shi da Baba Sule na ce babu komai sadaka ce anan yake yi mini albishir din fitowar Hadiza kwana biyu da suka wuce gwamnati ta yi yasa da sasaauci a gidan gyaran halin da take zaune duba da watan da muke ciki an duba iya adadin shekaru da zamanta a gidan Allah Ya taimakata ta shiga cikin wad'anda suka fito ba tare da tsananta bincike akan lefin da ta aikata ba. Magana ce ta gwamnati bisa sahalewar gomna duk abinda aka ce hukuma a gidan duniya ai k'arshen magana kenan sai dai idan an je can lahira anan Ubangiji zai fitar da sakamako. Yana gaya mini tana nan koyaushe cikin sallar dare da ro'kon Allah gafara kuma duk ta tsangwami kanta bata fitowa ta yi walwala da jama'a.
Tausayinta ya kama ni sosai na ce ya gaya mata zan kira ta a wayar Ummansu mu yi magana idan na yanke shawara dama dole hakan ta kasance fita ma gagararta za ta yi tunda kowa ya san abinda ta aikata jama'a za su yi ta kallonta wasu ma har su jefe ta ko kuma a farauci rayuwarta kamar yadda suka farauci ta wani ita da abokiyartata Hajiya Alili da har yanzu ba san a ina ta boye ba.
Da yamma ranar Hajiya Saratu ta zo domin yi mini ta'aziyya ba ta samu zuwa ba a lokacin rasuwar  sakamakon ciwon kafafun da ta d'an yi a cikin kwanakin.

To da daddare kafin mu kwanta nake gaya masa halin da ake ciki tare da yi masa godiyar bisa alherin da ya yi.
Bai yi jayayya ba ya amince mini akan abinda nake so yana fad'in Hadiza 'yar uwata ce kuma gida dai sunan nasa ne amma ni nake rayuwa a ciki  da yarana tunda har na aminta da zama tare da ita shima yana yi mata murna samun ku'buta tare da addu'ar Allah Ya tsare gaba.
Ban samu yin waya da ita ba sai da gari ya waye tukkuna na gaya mata hukuncin dana yanke ta dinga kuka tana yi mini godiya tare da jaddada mini a shirye take domin na ce zan turo Magaji ya zo ya d'auketa mu zauna tare a gidan Hajjan kafin lokacin da za mu tafi can abujan. Ummansu  ta yi kuka kamar me a waya tana yi mini godiya ina fad'in hannu baya rub'ewa a yanke a yar Hadiza har yanzu tamu ce kuma 'kaddara tana kan kowa farincikin ayadda ta tuba take kuma neman afuwar Ubangiji lallai shi din mai gafara ne da jin kai. Kuma hakika fitowarta da wani lamari da yake kwance wanda mu ba mu san shi ba, da ya so da tun farkon lamarin ya kar'bi rayuwata don haka ni ma daga nawa b'angaran wannan kad'ai zan yi mata domin ta samu sassaucin zuciya killaceta a waje daya da ababen more rayuwa da kula domin ta dawo nutsuwa da hayaccinta. Shi kansa Babanmu rasa abinda zai ce ya yi domin da da farko ya nuna rashin yardarsa yana fad'in Hadiza ta yi girman da za a ce ta je ta zauna mini a gida ita ba yarinya k'arama ba. Akwai wani abokinsa matarsa da ta rasu ya buk'aci auranta yaransa tara marayu a yanzu auran shine rufin asirinta. Na ji gabad'aya lamarin bai kwanta mini a rai ba abokin Babanmu ai da shakarunsa kuma ko auran za ta yi a yanzu akwai buk'atar zuciyarta ta nutsu kada don an ganta cikin ibtila'in rayuwa a yi kokarin k'àrasa kassara mata rayuwa saboda bata da jayayya tunda mafaka take nema kai tsaye zata amince ko da ranta baya so.
Da yake ni ce na zo da maganar kuma nake buk'ata sai ya ha'kura ya amince mini. Anti Yagana ma ba ta yi jayayya ba ta nuna goyon bayanta dangane da hakan tana fad'in idan ta huta hankalinta ya dawo jikinta shekara daya zuwa biyu sai ta dawo gida ko kuma ta yi aure.
Akan haka muka tsaya kuma a ranar da yamma Magaji ya je ya d'aukota duk abinda ya faru ga rayuwarta na labartawa Hajja har da kuka tana fad'in sannu baiwar Allah kin ga jarabawa Allah Ya yafe miki mu kuma mugun ji da gani Ubangiji Allah Ya kare mu.
Hadiza tun a gidan Hajja ta fara yin dawainiya da su Hasan sai ta kar'be ni tunda da tare muke yi da iyami Hajja na dan yin abinda za ta iya amma zuwanta sai ta kar'be ni a duk sanda zan daga ido na kalleta sai k'walla ta cika mini ido. Mace 'yar garu da ta samu gatan uwa a lokacin da take sharafi da jiki mai kyau ta koma haka Hadiza ko da can ba ni da abinda zan nuna mata tunda ta yi tashen 'yan matanci kuma bata ta'ba yin saurayi talaka ba masu arziki ne daidai gwargwado ne suke zuwa neman auranta. Fara ce tas haka suke dukansu tunda Ummansu ma fara ce ta fi ni haske tana da kirji sosai a wancan lokacin ni kuma baya na fita da tsayuwar hallita mai kyau dalili ni jikina ta ko'ina dumur yake koda na yi haife-haife nan babu inda ya saki ya ragaje alhamdulillahi. Ita kuma irin jikin Ummansu ne da ita a sake amma akwai kirji cikakke a lokacin budurci ba yanzu da suka risina ba

saboda wahala da shekaru tunda kwanaki biyar kacal ta ba ni ba wani nisa a tsakaninmu amma wallahi ta fi ni tsufa hakan yana da ala'ka da wahala da rashin samun hutu zullumi fargaba da rashin 'koshi. Alhamdulillahi ni kam kullum cikin hutu nake da kuma cima mai kyau tunda tsakani da Allah idan ba a zaman makokin nan na Gwaggo ba sai na ce na fi shekara tara rabona da shan ruwan pure water sai da mugun dalili ko maiduguri na je gidan anti Yagana ruwan gora Babansu Fadila yake sayo mini har na gama zaman da zan yi a gida.
Rabon zakkar da ya fitar  ta zagaye dangina kaf daga can maiduguri Baban Saude ne wakili nan kuma Sunusi ne wakilinsa babban yaron baba Sule duk wanda sako ya same shi sai ya kira ni a waya ya yi godiya domin babu hanyar da za su same shi su yi masa godiya Y
'yan biyun gidanmu da su fari ana gobe za mu tafi suka zo muka yini tare muka sha ruwa cikin sakewa a bangaran da nake har ya shigo ya same mu muna raha abin mamaki sai ya zauna a cikinmu kunya kuwa duk ta kama su mussaman Hadiza da ta kasa daga kanta ta kalleshi dalilin abubuwan da ta yi a can baya ta dinga kar'be masa kudi tana shirya k'arya. Ya dinga jan ta da magana duk domin ta sake amma ina ta kasa kanta a kasa har ya tashi ba ta dago ba.
Sahura ba ta samu zuwa mun yi sallama ba sai dai ta kira ni a waya ta yi mini godiya sosai domin itama ta kar'bi zakka da kayan abinci rigijib a wajan aikinsu
Komai nasa cikin tsari da lissafi duk yadda ya yi mini haka ya yi a b'angaran Hauwa domin da kunnena na ji Hajja na waya da Inna Uwani kan kayan abincin da aka fitar musu da zakkarsu ta ce abincin dai a sa direba ya kai mata can bauchi kudin kuma bayan sallah za ta kar'ba sai a lokacin ne ma Hajjan ta san da cewar har yanzu tana abujan ba ta koma gida ba.
Ranar da azimi ya yi ashirin muka tafi bayan mun yi sallama da Hajja Yusi ya na gaya mini cikin sallah zai zo ya yi mana kwana biyu cikin 'yan uwansa na ce to Allah Ya kawo shi lafiya.........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*168*
Abinda ya so ya d'an ba ni mamaki bai wuce ganin ya tafi gidanta ya kwana ba. To matarsa ce har yanzu tunda bai saketa ba a tunanina ni zaman da nake yi ba su samu matsaya ba har yanzu a cikin rikicin suke tunda bai ta'ba nuna mini cewar sun daidaita ba a lokacin dana tambaye shi ina yara bayan tafiyar masu aiki umara a takaice ya ce mini suna gidanta. Ni da Hadiza muka kwana a gidan da safe muka tashi da aikin gyare-gyare zuciyata ta'ki tsayuwa waje daya sai tunanin yadda aka yi suka iya shawo kansa cikin k'an'kani lokaci duk da fusatar da ya yi akan lamarin to ko shine manufar rashin tafiyar inna Uwani a lokacin da ya koma bayan mun zo duba Gwaggo

nake tunanin suka daidaita tsakaninsu amma abin ya ba ni mamaki sosai. Na yi kokarin dannewa saboda samun kwanciyar hankali da nutsuwa  zuciyata tana gaya mini gwara duk rintsi su shirya domin ko da ya yi musu abinda suke so zai iya auro wata tunda ya riga ya saba zama da mata biyu. Amma yanayin yadda suka dinga jujjuya maganar ne ita da uwarta ke ba ni mugun mamaki tabbas Inna Uwani tsufa ya yi gardama kuma an yi fad'uwar ba'kar tasa.
Bai shigo ba sai wajan d'aya da wani Abu yanayin shigar da ya shigo mini da ita ya tabbatar mini da cewa daga massalaci ya fito. Babu wani abu dana nuna masa a fuska ya zauna a falo cikinmu ni da Hadiza har k'asa ta durkusa ta gaishe shi Hadiza wani irin ladabi ta koyo a gidan gyaran halin da ta zauna Ya amsa kuwa cikin kulawa ta tashi tsaye da Usaini a hannunta za ta nufi bedroom dina Hasan ya sanya kuka yana mika mata hannu wai sai ta d'auke shi. Kwanaki shida kacal a tare damu yaran sun yi sabo da ita.
Uban ya kar'be shi daga hannuna yana fad'in." In ban da rigima da wane hannun za ta d'aukeka ka ci girma mana."
Ya dinga tsala ihu yana zillo tare da mika mata hannu shi kuma Usaini na kwance a kirjinta ya yi luf.
Na kar'be shi daga hannunsa abin mamaki ya'ki yarda wai lallai sai ta d'auke shi, kishi dai irin nasu. Haka duka ta ciccibe su a 'kui'binta ta rirrikesu da hannunta ta nufi bedroom dina tana dariya yaron ya yi shiru ya daina kuka da zanbarwa.
Ya dube ni a nutse yana fad'in." Tausayi take ba ni sosai 'yar uwar nan taki Giwa."
A takaice na ce." Mun gode sosai Allah Ya kara rufin asiri?"
Ya zuba mini ido babu halin ri'ke hannu ko runguma saboda muna cikin ibada tunda ma Gwaggo ta rasu muka fara azimi ba mu yi wata kwanciyar kirki ba saboda abubuwa da ya wasa da suka sha kansa. Ya sauke ajiyar zuciya ba tare da ya janye idonsa daga kaina ba ya ce." Zan tura miki kudi kamar yadda muka saba kowace shekara
 domin ki sayi abinda ki ke buk'ata na sallah.
Yara Hauwa ta saya musu wurin  k'awarta suna wurinta ta ce a gaya miki idan an jima suna shigowa yi miki gaisuwa. "
Na ce." Ban gane hausar ba?"
"Ina nufin kayan sallar yara takalma da riguna na kanti an saya akwai saura wurin telansu zai kawo cikin satin nan inshallah."
Na d'an yi jim ina nazarin maganarsa a wannan karon kenan ita ta kar'bi kudin ta saya musu kayan wajan k'awarta sanin da na yi duk salla marigayiyace Maryam ke yi musu wannan hidimar amma dai har yanzu telansu da yake yi musu d'inki yana nan shi yake yi musu  ko bayan rasuwar wadda ta d'auke shi aikin ya cigaba  domin ni ma wasu lukutan yakan yi mini d'inkin amma ba sosai ba watannin baya ne da ya ce a fitar da kayansu gabad'aya ya sanya a aka kawo musu sabbin 'yankati to me hana wannan karon ma bai sanya an kawo musu ba.
A tak'aice na ce." To shikkenan." Ya dube ni yana fad'in.'' Ko hakan bai yi miki ba ne?"

Na ce." Ko bai yi mini ba ai dole na ha'kura tunda zaman lafiya nake so ko, amma ai da can ba ita take saya musu ba."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." To yanzu don ta nuna ra'ayinta ai ba lefi bane ki duba kayan sosai idan ba su yi ba sai a canza musu
ku dai zauna lafiya da juna, ita mun samu daidaito da ita kuma mun yi alkawari a zaman da muka yi domin har sai da kawunta ya zo mun zauna da ita Inna Uwanin ta yi alkawari kan cewa za ta gyara tare da ko'karin kawo zaman lafiya a junanku.''
Shiru na yi ban iya ce masa komai ba saboda mamaki.
Ya tashi ya hau sama ban bi shi ba na yi zamana ina nazarin yadda abubuwa suke canzawaa daga wannan sai wannan zuciyata tana gaya mini kudi ta kar'ba masu kauri a hannunsa domin ta 'karu tunda dama neman hanyar da za ta dinga samun kudi take yi.
Ita kuwa wadda ta rasu tana yi ne da dukiyarta bata neman kwabonsa ita nata salon kenan tunda tana da arziki. Ita kuwa Hauwa na tabbatar da cewa ta yi hakane domin 'karuwarta.
Da yamma muna kicin tare da Hadiza muna shirin abu bude ba'ki suka shigo..
Na bar ta a kicin din goye da Hassan ya yi bacci na fito falon na same su a zaune Inna Uwani ta d'auki Usaini yana saman cinyarta da abin wasansa a hannu.
Na d'an saki fuskata ina yi musu barka da zuwa na zauna kujerar dake kallonsu yaran gabad'ayansu suka shigo Khalil twins da Minal wurina suka rugo a guje k'ananun shi kuma Khalil din yana ta dariya kafin ya d'an risina yana fad'in." Mama ina yini?"
Na amsa da kulawa ni ma ina dariya na ce." Kai ya na ga duk ka yi zuru-zuru azimin nan fa bai wajaba a kan ka ba."
Ya sa dariya yana fad'in." Ko bai wajaba a kaina ba ba zan asha ko daya ba Mama.
Minal tana ta'ba mini cinyata ta ce." Mama ni kin ga haka na yi." Ta had'a yatsunta biyar ta d'ora d'aya a kai."
Na bude baki cikin mamaki ina fad'in." Da gaske." Karaf Usai ta buge hannun tana cewa." Ma'karyaciya ko daya ba ta yi ba wallahi." Cikin wasa ta yi maganar don har tana dariya ma.
Abinka da yarinta ita kuma Minal din sai ta fashe da kuka tunda dama dangwalolo ce. Nan da nan Hauwa ta 'bata fuskarta na ji lokacin da ta ja tsaki mai tsayi.
Ina Uwani na fad'in." Ke kam Usaina kin fiye saurin hannu wallahi menene abin duka Kuma?"
Khalil da sauri ya ce." Ba dukanta ta yi ba fa Inna."
Hauwa ta harareshi tana fad'in." Ba mu da ido ko kaine kake da Ido don ubanka zaman da suka yi a can ma kenan ba dukanta take yi ba."
Ya yi shiru yana yin fuskarsa ya canza.
Na ce." Ai saurin hannu gare ta na gaya mata kuma 'kanwarta ce."
A d'an sanyaye ta ce." Ban doke ki ba ko Minal?"

Sai ta d'aga kanta. Tsakanin yara ba a shiga Usai din ta sanya hannu tana goge mata fuska.
Daga haka na ce." Ku je dakinku ku zauna kafin mu gama gaisawa..
Suka kama hannunta suka bar wajan.
Cikin kulawa na fara gaishe da Inna Uwani itama ta amsa a d'an sake ta yi mini ta'aziyya tare da jajanta mini rashin da aka yi. Haka itama Hauwan mun gaisa babu yabo babu fallasa ta yi mini gaisuwa kafin ta dubi Khalil tana d'an harararsa ta furta." Ba ni ledar kayan nan?"
Na dube shi da sauri wata babbar leda ce da ya shigo da ita sai ya ajiyeta gefan kujera. Ya d'auka ya mika mata ta kar'ba kafin ta kalle ni tana fad'in." Babansu ne ya bada kudi aka saya musu 'yan kanti wurin Sadiya wannan shekaran ta kawo kaya sosai ai baki mance ta ba ko?"

Na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biyani hakkina ba

Na gyada kaina a nutse ina fad'in." Ban mance ta ba." Sai ta mi'ko mini tana ce wa." Na ga sun yi kyau sosai set takwas ne kowanesu hud'u."
Na kar'ba na ajiye a gefena ina fad'in." To madallah."
Suka amsa tare kafin ta cigaba da cewa." Takalma ne kawai babu sizi d'insu a wurinta shine ban ce ta aiko ba amma gabad'aya yaran an saya musu da mayafai sauran suna wurin telansu yadda ya ce cikin satin nan zai kawo."
Na ce." To shikkenan wannan na Hasan da Usaini ne kenan?" Ta gyad'a kanta na ce." Ina na su Hassana?" Sai ta d'an diririce kafin ta ce." Yana can gida zan aiko miki da su gobe ko kuma an jima da daddare.
Shiru na yi ban ce komai ba. Hadiza ta fito daga kicin da yaron a bayanta cike da walwala a fuskarta ta zauna suna gaisawa. Inna Uwani ta yi caraf ta ce." Wannan kamar 'yar uwar nan taki ko?"
Na ce." E, itace Hadiza ba?" Sai ta ri'ke bakinta tana fad'in." Itace ta lalace haka sai ka ce wadda take d'auke da siga ko kanjamau!"
Maganar ta dake ni sosai cikin fad'uwar gaba na kalleta bakina sai ya yi nauyi na kasa ce mata komai.
Hadiza cikin gaggawa ta tashi ta bar wajan domin itama da alama maganar da Inna Uwanin ta yi akanta ba ta yi mata dad'i ba.
K'asa na yi da kaina zuciyata na hantsilewa akwai dalilan da suka sanya nake d'agawa matar nan 'kafa ba wai don tana uwar kishiyata ba ina kallonta kamar Hajja tunda ciki daya suke amma an kusa kaiwa matakin da zan fara mayar mata da raddi a duk lokacin da ta yi mini wani rashin hankalin.
Ya sauko ya same mu a zaune a falon ya zauna gefana yana kallon Inna Uwani da ta k'irkiri yi wa Usaini wasa har da yi masa rawa tana dariya shima yaron yana yi. Hakan kuwa ya yi masa dad'i sosai aka ce wai mai d'a wawa sai ya shiga washe bakinsa tana fadin." Yara duk sun yi wayo kamar ba biyu ba sun yi kyau uwarsu na da kafar nono mai kyau."
Ya ce." Haka aka yi goyon 'yan uwansu ma." Ta miko mini yaron tana fad'in." Ai ban mance ba. Ubangiji Allah Ya raya mana su domin su zama cikon addinin musulunci duniya kuma ta amfana da su."

Ya dinga amsawa da Amin ya rabbi Inna Uwani Ina godiya sosai."
Suka tashi tafiya bakina ya mutu kwarai dangane da salon da suka shigo da shi. Da k'yar na ce su gaida gida ya tashi ya bi bayansu kafadarsa sa'be da yaron.
Ina nan zaune ya dawo ya zauna cikin walwala a ganinsa mun fahimci juna tunda gashi har ya sakko ya gan mu kuma yaronsa na hannu Inna Uwani tana yi masa wasa wannan ne dalilin da ya assasa masa annasuwa da farinciki bai san da cewa wani sabon salo ba ne.
Na zazzage kayan yaran ina dubawa. Eh rigunan manya ne kuma sun yi kyau sosai zan iya kar'ba na yi musu amfani da shi tunda an riga an saya na su Hassana ne ban ga ni ba. Na juya ina tambayarsa "Ta kawo mini kayan su Hassan ban ga na su Hassana ba?"
Ya dube ni da kulawa yana fad'in." A a ba ta had'o da su ba ne?"
Na ce." Eh" Sai ya dan yi jim kafin ya nutsu yana kallona ya furta." Ki bar mata su su yi sallah a hannunta idan hutun makaranta ya 'kare sai su dawo gabad'aya jiya ta fara gaya mini cewa tana son yaran su yi mata hutu.''
Girgiza kaina na yi tare da cewa." A a, yaranta dai ka kai mata su amma nawa yaran su dawo gidansu ba ni son abinda zai daga mini hankali a yanzu dai cikin ibada muke abinda ba zai yiwu ba ne.''
Ya d'an 'bata rai yana fad'in." Ke dai duk ta inda aka biyo miki ba a yi miki gwaninta Amina menene lefin nan da can kuma duk gidana ne akwai buk'atar a ko'ina yarana su sake su kuma yi sabo, ki yi hakuri ki bar mata su hutu kawai ta buk'aci da su yi a hannunta sai su dawo, ki duba kawaicin da ta yi miki a kan nata yaran mana."
Na sake girgiza kaina a karo na biyu na furta." Na gaya maka fa ba zai yiwu ba ai ni ban buk'aci zaman yaranta ala dole a tare da ni ba. Kai ka kawo mini su kuma ba zan hana su zama ba tunda gidan ubansu ne. Maslaha anan shine ka kwashi yaranta a kai mata tunda zahiri ana shiga hakkinta alamu sun nuna kad'aici ya isheta hayaniyar yara take buk'ata. Kowa ya rike nasa shine zance na gaskiya."
"Kamar yadda na isa na bata umarni ta bi ke ma haka za ki bi. Na gama yanke magana yara za su yi hutu gidan Hauwa idan sun 'kare su dawo ku cigaba da zama gabad'aya tuntuni yaranta dake suka saba kuma suna kaunarki babu wani dalili da zai sanya ni raba su dake saboda suna sonki itama ta yarda da hakan."
Yana gama fad'in haka ya d'ora mini yaron saman cinyata ya kama hanyar samansa yana magana." Idan Hakan bai yi miki ba ni ma sai ki raba ni biyu ki d'auki b'angaran da kike so a jikina sai ki bata rabin tunda duk a kaina kuke wannan 'kiyayyar junan idan na mutu kowa zai huta ai."
Na dinga kallonsa har sai da ya gama hawa steps na daina hangensa na dawo da kallona kan yaron da yake ta zura hannunsa cikin rigata nono yake nema. Babu kuwa halin ba shi domin tunda suka fara wayo nake had'a musu kamu irin wanda Sultan ya sha yana kan matakinsu balle yanzu da ake yin azimi ba ni yarda su tsotse ni da tsotsan jaraba.
Bai sauko ba sai daf da za a sha ruwa mun gama aiki Hadiza na gyara kicin din muka dinga jin kuka a falon na fito da saurin gaske. wanda ya yi daidai

da saukowarsa Minal ke kuka tare da Sultan Hauwa ta turo mai aikinta Ladidi wai su tafi tare. Sauran sun yi cirko-cirko. Kuka fa sosai Minal ta ri'ke hannunsa tana fad'in." Baba ba kaine ka ce mu zauna a can ba sai Mama ta dawo, to ina za mu je ai nan ne gidanmu Ladidi za ta d'auke mu."
Sultan da tafiyarsa ta yi k'wari sosai ya taho da d'an gudu ya rige gefan rigar uban yana kuka ya sunkuya ya d'auke shi yana kallon Khalil ya ce." Je ka dauro alwala lokacin sallah ya yi." Yaron ya juya da sauri ya bar wajan.
Sai ya dubi Ladidin yana fad'in." Je ki abin ki idan an jima zan shigo da yaran."
Ta risina da sauri kafin ta juya ta kama hanyar fita.
Khalil ya fito da alwala sai ya dire Sultan din a kasa ya ce." Ri'ke hannunsa muje massalacin tare."
Ya yi gaba da sauri su kuma suka bi bayansa..
Na dube su Usaina ta ri'ke hannun Minal din tana zaune dirshen 'kasan ties amma kukan ya tsagaita. Na ce." Ya isa haka ta shi kuje ku yi alwala a yi sallah sai a ci abinci ko?'
Ta daga mini kai tana sakin ajiyar zuciya ta tashi 'yan uwan suka tasa 'keyarta zuwa dakinsu.
Daga ni har ita Hadizan cikin damuwa muke amma ni na yi kokarin ganin na kawar da tawa damuwar domin samar mata da kwanciyar hankali. Ba wani abu ba ne yake nukurkusarta face maganganun da Inna Uwani ta gaya mata d'azu. Bud'e baki ma da 'kyar ta iya saboda damuwa. Babu komai ai rayuwace duk wanda ya yi wa kaddarar wani dariya watarana Ubangiji shima zai jarrabe shi da abinda zai zama abin nuni da zind'e a idanun jama'a. A fakaice na d'an dinga jan hankalinta da wayo da rarrashi ta ci abinci tana ta nuku-nuku da hawayen dake ma'kale a kwarmin idonta.
Tunda yau ma din a gidanta zai kwana ban tsammaci sake dawowarsa ba mussaman tunda ga irin rabuwar da muka yi wajan goma da ashirin muna falo muna kallo gabad'aya har da yaran ba su kwanta ba. Ya shigo ri'ke da hannun Sultan yana ta sauke ajiyar zuciya yaro idonsa ya yi jawur da kumburi almar ya ci kuka ya k'oshi. Khalil dake biye a bayansu Fadi." Yake yi ga ta can Usai din je ka."
Ya kuwa tafi wajenta da sauri yana sauke numfashi. Na dubi Khalil din ina fad'in." Me ya same shi?"
'yar dariya ya yi kafin ya ce." Wai ba zai kwana a can ba shine yake ta ihu yana kiran Usaina."
Abin ya ba ni dariya da tausayi. Na d'an janyo hannunsa ya taso ya tsaya kusa da ni tare da dora hannunsa saman cinyata na ce." Anan kai ma zaka kwana ko Sultan?"
Ya d'aga kansa. Na furta." Ashe kwanciyar dole kuke yi a can din ko Khalil?''
Shiru ya yi bai ce komai ba sai ma ya yi k'asa da kansa.
Hadiza ta mike tana fad'in." Bari a gyara musu shimfid'a." Ta nufi d'akin nasu da sauri.
Na ce su tashi su bita su canza kaya sannan duk su yi alwala kafin su kwanta.

Duk abinda ake yi yana tsaye yana kallonmu bakinsa ya mutu da alama ya rasa abinda zai ce. Bayan shigowarsu na dubi Khalil Ina fad'in" D'auko Usaini ka biyo ni dashi d'aki." Dama Hasan yana ri'ke a hannuna na tashi da shi a kafa'data kai tsaye bedroom dina na nufa ba tare da na sake kallon wajan da yake tsaye ba, a haka yara za su yi hutu a wajanta na kwanaki suna yi kamar za su mutu saboda kuka ashe da babu kowa a gidan ha'kuri kawai suka yi suka zauna tunda yanzu na dawo kuma sun nuna mata basu san wata ba bayan ni. Da nata da nawan gabad'aya don ni sai nake ganin twins ma sai su zauna a hannunta ba tare da koke-koke ba nata ba su zauna ba Minal dai da Sultan sun tsaneta wallahi abin har mamaki yake ba ni. Ita Minal yadda take bala'in sona shine abinda yake sanya mini sanyin jiki shi kansa Uban na lura da yadda jikinsa ya mutu abin ya fi karfinsa Hauwa ta haifar mini yara Allah mai iko......✍
*GARKUWAR MATA*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*169*
To ban san abinda ya kasance a tsakaninsu ba  washe gari dai da misalin sha d'aya da wani abun Ladidi mai aikinta ta kawo musu kayansu kaf na can wanda suka yi amfani da shi bayan tafiyata kano da kayan sallar tasu da suke a hannunta pants takalmansu da kayan kitso abin wuya da hannu kowanne da na shi da alama duk ta had'a ta yi order din wurin Sadiyar gabad'aya girkina ne a ranar bai shigo ba sai bayan magriba tukkuna ya buk'aci abin bud'e baki na hada masa babu wata sakewa don sai nake ganin kamar akwai abinda ya boye mini. Kunun tsamiya muka yi da k'osai yadda ya kusa shanye dogon jug hakan ya tabbatar mini da cewa kunun ya yi masa dad'i k'osan ma ya ci fiye da biyar saboda sakin manya muka yi. Ya sha zo'bon dana had'a daidai gwargwado ya kammala yana godiya ga Allah kafin ya dawo da hankalinsa gare ni
Na yi shiru ina sauraransa." Akan maganar da muka yi dake kwanakin baya kin ce kina buk'atar a musanya miki wannan kamfanin ko?"
Na gyad'a kaina a nutse na furta." E, idan zai yiwu ba wai na raina kyautar ba ne kawai dai na fi gane business din da nake yi ina ganin idan na sake samun wani reshen anan za a samu alheri."
Ya ce." Shine dalilin da ya sanya ai na sake tambayarki tuntuni nake ta shawara a kan hakan kyautar za ta koma kan Hauwa tunda ni ba ni so a tashi kamfanin ko babu komai kadara ce mai girma da ta kafu tunda a 'kalla da kafa kamfanin zuwa yanzu ya haura shekara goma sha shida duk yanzu muna kan aikin fad'ad'a waninsa ammana akwai buk'atar shi d'in a cigaba da aiki da shi. Na mallakawa Hauwa shi ke kuma akwai tallan wasu tsoffin shaguna da aka yi mini cikin kasuwar wuse din idan mun kammala da masu shi zan sanya ma'aikata su rushe tare da sabunta shi zuwa plaza din kamar yadda ki ka buk'ata a k'alla dai za a iya samun shaguna sha biyu 'kasa shida

sama shida a hankali idan Ubangiji Allah Ya sanyawa abin albarka sai ki yi wadda ta fi wannan din ko?''
Na ce." Hakane na gode sosai Allah Ya saka da alhari ya kara arziki ya kuma jikan iyaye."
Ya dinga amsa cike da jin dadi yana jifana da wani irin kallo wanda na gama fahimtar ko na menene.
A daran kam na kar'be shi sosai kuma na yi kokarin ganin na yi masa bajinta wajan ganin na bashi farinciki yanayin yadda na tallafe shi ya k'ara dilmayar dashi cikin yanayi na shau'ki da sambatu irin wanda ba a tonawa wannan lamarin ai ba zai fasu ba idan da rai da lafiya a jikin gangar jiki.
Kwanaki biyu bayan wannan su Baba Tabawa suka dawo murna a wurin yara ba a cewa komai tsalle mussaman Sultan ya rirriketa tana dariya itama ta rungumeshi bakinta kamar gonar audiga gabad'aya sun canza da wata iriyar nutsuwa alamu ibadar da suka gudanar ta samu karb'uwa a wurin Ubangiji domin fes suka dawo da wani annuri na mussaman a tattare da su.
Dawowarsu ta sake bud'e wani sabon babi na farinciki a gidan ya kasance koyaushe cikin wasa da dariya da juna mussaman da bikin sallar ya gabato Mairo ta tsefewa yara kitso an wanke tas Taburni itace makitsiya Lad'ifa mai lalle saura kwana uku sallah ta zo ta yini tana yi wa yara washe gari ta dawo ta yi mini tare da Hadiza aikuwa tasha kudi wurin maigidan mussaman da ya ga na yaran ja da ba'ki ya fito sosai ya dinga duba kafafun nasu yana murmushi ta had'a kayanta ta tafi cike da farinciki dubu dari biyu kudin lalle kawai duk da Hajiya Maryam ta saba yi mata kyauta amma wannan ta yi mata bazata domin duk zuwan da take yi mini lallen ni nake sallamarta yau sai ga shi rabonta a ya rantse, ta samu kudi da turaruka da sabulai na hada mata da gyale mai kyau.
A daran mai dinkinsu ya aiko da shi kowanne k'alla gudu leces biyu a tamfa daya sai shadda daya wadda ta ci uban aiki abin mamaki har da na masu aiki set biyu Hadiza kuma aka yi mata uku manyan atamfofi. Sai na 'kara mata da lece daga cikin kayana dake d'inke wanda ban sanya ba. Takalmi na bata set biyu masu tsayin dunduniya duk sabbi da abin wuya da hannu.
gaskiya babu lefi ya yi kara ya kuma nuna halin dattako domin duk wanda yake karkashina yana sane da shi yana kuma ko'karin fitar da hakki ban ta'ba tunanin zai yi wa Hadiza d'inkin sallah ba duba da ganin yadda abubuwa suka yi masa yawa ashe yana sane da ita a gidan ya kuma fitar mata da hakkinta.
Wannan shine abinda ya gudana bayan ramadan mun yi bikin sallah cike da annashuwa da farinciki tun daga kan masu aikin gidan maza dake waje da na cikin gidan su Baba Tabawa kowa ya kasance cikin nishadi da jin dad'i. Washe garin sallah yaran gabad'ayansu gidan Nusaiba suka yini bisa jagoranci Adam sai magriba suka dawo ta had'o su da snacks da yawa da kud'i Babansu ya dinga fad'a wai me yasa za ku kar'bo mata kudi ina lefin hidimar da ta yi musu. Na ce sallah ce ai don ta ba su kudi ba lefi ba ne.
Sun je gidan Hauwa amma ba wasu wani jima ba suka dawo itama ta had'o su da tarin chocolates masu yawa har da sa'kon gaisuwa zuwa gare ni. Cikin raina na ce tunda kin fara dafe wasu kadarori ai fitina ta kusa zama tarihi

kyautar kamfanin da ya yi mata ya taka muhimmiyar rawa wurin dakushe mata damuwa tun bayan abinda ya faru ba ta sake fito da wani salon ba ga yaranta har yanzu suna hannuna.
Salim ya zo hutun sallah tunda yana can legos yana aiki a sabon kamfanin da suka bud'e shi ya dinga fita da yaran wuraran wassani ashe lokacin da Mamansu na raye haka yake yin jigila da su duk shekara ya ce ma saboda su ya dawo domin yin bikin sallah.
Sati daya ga sallah Inna Uwani ta shigo har gida wai sallama ta zo yi mini zata tafi. Na bata turaman atamfofi uku da kudi dubu ashirin na ce ta kara guziri. Babu jin kunya ta dinga yi mini godiya daga lokacin na sake tabbatar da cewa muguwar kwad'ayayyice mai son abinda duniya Allah ne ka'dai yasan abinda Hauwa ta had'a mata domin tafiya dashi wanda kuma nake da tabbacin cewa shi kansa maigidan ya yi mata sallama mai kyau Allah Ya kyauta ya rufa asiri yanzu zamani ya lalace tundaga lokacin dana ganta a shekarun baya tana yi masa yarfen magani a kafar bane na tabbatar da cewa bata da hali kuma bata tsoron Allah kuma za ta iya aikata komai a kan biyan buk'atarsu tunda ai ba zata za'be shi ba ta ajiye 'yarta ba duk wannan jidali da koke-koken da take yi akan abin duniya ne tana taya 'yarta kishi tana kuma yi wa 'yar uwarta ciki daya zagon 'kasa a yanzu idan ya fadi ya mutu

Na kudi ne littafin kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

damuwarta kad'an ce tunda ba ita ta haife shi ba mahaifiyarsa da yaransa sune suka yi rashi. Bala'in damuwar da suka shiga a lokacin da cikin nan ya zube ba zai misaltu ba domin an same shi ne da k'yar ni ma na gazgata maganarta bai fiye kwanciyar aure da ita ba domin da yana yi da ita ka'in da na'in zan samu sasaauci ta wannan fanni amma Allah ne da kullum duk ranar girkina sai ya neme ni idan har ba mu yi sunna ba to akwai dalili mai karfi wanda ya assasa rashin faruwar hakan koyaushe cikin doki da sambatuna yake ya sha fad'in shi kullum tamkar sabuwar budurwa nake a wurinsa abin ya yi ta ba ni mamaki haihuwa biyar ciki har da biyu sau biyu tun ina d'aukar maganarsa da dad'i ne na shau'ki har na gazgata domin da dukkanin gaskiyarsa yake fad'in hakan. To wannan shine dalilin da ya sanya su shiga tashin hankali a lokacin da cikin ya lalace har suna neman rabuwa saboda ganin kada a yi biyu babu yanzu kuwa na tabbatar da cewa ko da bata samu kula ta fannin auratayya daga wajansa ba to za ta cigaba da hakuri tunda ta fara samun abinda take buk'ata.
Hadiza wata uku a gidana ta murmure haskenta ya dawo ta yi ki'ba jikinta ya fara cikewa domin dawowar masu aikin gidan na hana ta yin wata wahala mai yawa sai dai duk da haka takan yi mini d'awainiya da yaran amma ba sosai take shiga kicin ba. Hakan ya yi mini dadi sosai domin ta fara sakewa na saya mata sabuwar waya domin ta kara d'eba mata kewa da mantar da ita irin wahalar da tasha a baya wajan zamanta a gidan kurkuku idan tana ba ni labari irin wahalar da ake sha ni kuka ita kuka daga karshe ma na ce ta daina gaya mini domin yadda ta ba ni labarin wani ma'aikaci da ya dinga

farautarta a lokacin da bai samu hadin kanta ba kullum sai ya sanyatawa kwashe busashen kashin band'akunan gidan da hannu kuma ba zai bata sabulu ta wanke hannunta ba haka idan an kawo musu abinci za ta ci bayan ta wanke da ruwa kacal tana gaya mini hannunta har sai da ya kame da d'oyin kashi. A d'akinsu kuwa mutum biyar sai da suka mutu saboda wahala tasha kwana da gawa a d'aki daya. Tun daga lokacin na ce ba ni son labarin saboda shiga tashin hankali nake yi na ce ta dage da addu'a tare da neman afuwar Ubangiji tsautsayi da mugun ji da gani asara tare da danasani Ubangiji Allah Ya kare mu.
Ranar wata lahadi ya kasance girkina ne maigidan bai tashi a bacci da wuri ba sai bayan sha biyu na rana yana tashi kuwa ya ce mini towo zan yi masa kuma da hannuna miyar zogale.
Aka duba kicin kaf babu zogale dole sai an shiga kasuwa Masa'udu ya je gida ganin iyalinsa tun sallah bai dawo ba shi kad'ai ne ya yi wannan nisan zaman domin ko su Taburni da Mairo satinsu hud'u suka dawo bakin aiki bayan sun je sun gaisa da iyalinsu tare da yi musu alheri daga cikin alherin wanda yake ri'ke da su.
Mairo da Hadiza sune suka shirya shiga kasuwa sayo zogale dalili Taburni da Baba Tabawa na aikin abincin rana. Suka shirya suka tafi Sukairaju ya kai su na hada musu da sautin tsamiya domin ya dingi shan kunun tsamiya ko bayan wucewar Ramadan sai ya ce a dama masa kuma ba dare ba rana duk lokacin da buk'atar son shan kunun ya bijiro masa wadda muke da ita tana daf da k'arewa da zo'bo tunda ana yi masa baya shan lemo mai gas.
Ba su yi awa d'aya ba kuwa suka dawo da komai da komai har da daddawa duk da ban buk'ace ta ba dalili ina da ita da yawa kuma mai mugun kyau wadda Hajja ta sanya aka yi mini ita mussaman lokacin haihuwar su Hassan da Magaji ya zo ya kawo mini kwalli da garafuni ya had'o mini da ita manya mai dadi a miya. Na ce ita din ma da suka sayo ba za ta'ki ba za ta yi amfani.
Tsaf na shirya masa towon shinkafa da miyar zogalen kamar yadda ya buk'ata na yi amfani da zallar tsoka na k'aramar dabba wurin had'a miyar da ta ji gyad'a da manja ta yi kyau sosai tana ta tashin k'amshi.
Cikin santi ya ci towon nan wurin malmala biyu kad'an ne bai cinye ba ina ta yi masa dariya ganin yadda yake sud'e hannu ina fad'in idan baka koshi ba sai a sa wani bai ce mini komai ba ya sud'e yatsun hannunsa tas ya shiga toilet domin yin burush

Bayan kwana biyu ya je gidan Hauwa ya yi kwanakinsa ya dawo yake gaya mini wata magana. Jikina ya yi sanyi sosai na zuba masa ido a hankali na ce." Hadiza fa ka ce, bai duba shekarunta ba kwanaki biyar kawai ta ba ni shekara arba'in da biyar muke ni da ita ba budurwa ba ce.''
A nutse ya furta." Akwai haramci ne cikin abinda Annabi Muhammadu S.a.w ya yi. Kada ki yi mana sa'bo hajiya shima Sukairajun ai ba saurayi ba ne ya ta'ba aure."
Na zuba masa ido sosai da mamakin jin maganarsa. Ya gyad'a kansa yana fad'in." Ya ta'ba aure shekarun baya a can mahaifarsa mutumin Zamfara ne kin ta'ba neman labarinsa a wajena?"

Na girgiza kaina a hankali ina cigaba da kallonsa sai ya cigaba da ce wa.'' Ya zo  nan kano cirani muka hadu da shi a titin Yahya gusau watarana tun kafin na yi shura a duniya yana sayar da fetur da kanikanci ya gyara mini mota a lokacin da lalace daga lokacin ya zama wanda nake bawa gyaran mota a duk lokacin da ta samu matsala muka yi sabo sosai har dai ya zama direbana kafin Ade da D'ahuru Sukairaju yaro ne mai Amana da nutsuwa da kuma girmama mutane ya gaya mini ya yi aure amma matar ta rasu wurin Haihuwa sasha zuwa garinsu wurin mahaifiyarsa kafin ta rasu. A duk lokacin da ki  ka gan ni tare da Ade to Sukairaju ya je ganin gida tunda duk 'yan uwansa suna can garin. Kuma ba na tsammanin Hadiza za ta girma shi sai dai su yi daidai a shekaru to menene aibu shine ya gaya mini da zata amince sai ya aureta shi yana sonta duk da na gaya masa abubuwan da suka faru a baya ya amince da hakan, don haka ina nema masa auranta a wajenki tunda kece uwar dakinta idan kin ce a yi za a yi."
Na yi kasa'ke ina kallonsa kafin na ce." Allah sarki wallahi ni kam ba ni da jayayya ko na kawo tasgaro muddin Hadiza ta amince zan fi son haka tunda har ka yabi kyawawan halayensa kuma ni ma na sheda hakan idan tana sonsa sai mu sha biki."
Ya yi dariya yana kallona kafin ya ce." To ta wace hanyar ki ke ganin za a sanar da ita halin da ake ciki, kin ga ni yayata ce da kunya na tunkareta ko."
Na d'an harare shi ina fad'in." Yayarka fa ka ce." Ya gyad'a kansa yana fad'in." K'warai kuwa ko da yini guda ta girme ki ai sunanta Yaya Hadiza a wajena."
Na yi kasa da kaina ina murmushi na ce." Shikkenan to ni zan gaya mata in sha Allahu rabbi za ta amince."
Ya furta." Da na fi kowa farinciki kuwa, ni kuma na yi alkawari zan yi iyakacin bakin kokarina.'"
Na gyada kaina ina fad'in." Ubangiji Allah Ya tabbatar da alheri." Ya kama hannuna yana cewa." Amin Ya Allah."

Ai a daran na same ta da maganar ta dinga dibi-dibi da 'kyar ta bud'e baki jikinta a mace babu wani karsashi da sukuni a tattare da ita ta kalle ni sai na hangi k'walla mai yawa cikin kwarmin idonta ta ce.............

In sha Allahu da ni daku mu sanya rai saura 8 chapter littafin nan ya kammala Allah Ya taimake ni ya kuma yi riko da hannuna dan isar Annabi. Ina miko godiya kwarai da fatan kowa ya sha ruwa lafiya. Ubangiji Allah Ya kar'bi ibadarmu ya 'yantar damu.....✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124... BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*

*170*
Shiru na yi ina sauraranta a yayin da take gaya mini abinda yake damunta har tana zubar da hawaye na damuwa da kunci tare kuma da fargaba. Jikina ya yi sanyi sosai domin dai na riga na gama fahimtar manufarta ba wai auran ne abin gudu   a wajenta ba abinda zai haifar bayan yin sa shine take ji wa tsoro da zullumi. To ai babu wata cuta da Ubangiji bai yi maganinta ba duk da infection wani irin ciwo ne da yake saurin dakusar da mu'amula da auratayyar da aka gina cikin tsananin so da sha'kuwa. Bayan rashin ha'kuri daga b'angaran ma'aurata abu na biyu da yake saurin kassara aure da lalatashi shine infection mussaman idan an yi katari da cewa macace taje da shi ta shafawa namiji abin sai ya yi muni da tsanani aure ya gurgu'de ba tare da yaje ko'ina ba. Hadiza na ga wautarta kwarai domin yanzu a k'alla da fitowarta daga gidan gyaran hali za a samu wata hudu to tun a lokacin ya kamata a ce ta sanar mini da abinda yake damunta domin neman magani ka'in da na'in. Zubar ruwa da kumburin gaba abu ne mai tsanani watarana zata iya wayar gari da susa tunda shi infection din idan ba a yi sauri an tare shi ba girmama yake yi har wasu su d'auka ta dalilin da rashin kula. Dama tun zuwanmu daki daban na ware mata a falon nan take kwana hakan ya sake yi mini amfani kywarai domin kuwa ina ganin da an yi had'akar toilet to wani zai iya d'auka wannan lamarin ba abin yin shiru ba ne kenan da wannan mas'alar ba ta zo ba haka za ta cigaba da zama da ciwo yana cin ta har sai ya zama babba irin wanda ake gudu. Tabbas babu maganar aure a wannan yanayin da ake ciki tukkuna sai an magance matsalar  idan ya so ko ma menene sai ya biyo baya babu amfanin gaggawa cikin kowane lamari kuma aure ba abin wasa ba ne idan har an yi shi to kowace mace tana bukatar zama a dakinta rayuwa ta din-din din ai  abinda ya fi infection ma za a iya d'auko shi a wannan gida domin da ta biyewa mazan dake bibiyarta wata'kila da da cutar 'kanjamau za ta dawo tunda yanzu maza da yawa sun lalace da neman matan banza ba wai ma'aikatan gidan ba manyan mutane ma da suke yawo cikin manyan riguna da motoci na alfarma tare da wata suttura ta Allah amma sai ka same su a hotels tare da karuwai suna amfani da su kuma suna da iyali a gida har da yaransu.
Haka dai na kwana cikin tunani da nazari da safe ashe yana hankalce da ni yana ta shirin fita ya ce na fito masa da takalminsa sahu ciki dake ma'ajiyarsa na fito masa da shi din kamar yadda ya buk'ata ya fesa turare ko'ina na jikinsa ya zo ya zauna gefena a nutse ya fara sanyawa k'afafunsa safa sai da ya kammala tukkuna ya dube ni amma bai ce komai ya gyara zaman gilas dinsa ya furta." Akwai abinda yake damunki Giwa ashe mun kai matsayin da yanzu za ki dinga yi mini b'oye -b'oye, an yi wani abu ne a gidan?"
Na kalleshi cikin kame-kame na furta." Wallahi akan maganar Hadiza ne ba wai boye maka nake yi ba abin ne dai yake buk'atar nutsuwa kafin wanzuwarsa."
Ya nutsu sosai yana kallona." To ai babu dole Amina shi aure na mutum biyu ne don Allah idan ba ta so kada ki tursasatata ai ba yarinya ba ce ita tana da

damar zabin namijin da ya yi daidai da rayuwarta shi da ya nemi auran nata zan gaya masa ya nemi wata."
Na gyad'a kaina a hankali na ce." Tana sonsa kuma tana son yin auran yadda ta nuna mini to amma kamar yadda ka ce babu munafurci a sha'ani irin wannan itama abinda ta duba kenan ta gaya mini tana da matsala tun fitowarta daga wancan gidan take ta fama da matsanancin infection."
Jim ya yi yana kallona kafin ya furta." Hakan ba zai hana a aureta ba tunda muna da asibitai da masu maganin gargajiya kowace cuta tana da maganinta don haka ku je asibiti tare ko kuma ku yi waya da Dr Sailuba duk abinda yake damunta a sanar da ita ni kuma na d'auki nauyi jinyyar in sha Allahu."
Na ce." Mun gode sosai Allah Ya saka da alheri, amma za mu fara yin na hausa ina da mai maganin Islamic masu kyau da inganci mafiakasari ina ji ana fad'in na Hausa ya fi kassara shi ya lalata tasirinsa har abada in sha Allahu za a yi dace Ina ganin idan har ta yi amfani da maganinta to duk wani nau'in sanyi za ta yi fitsarinsa."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." To hakan ya yi ki yi magana da ita din a jarraba Allah Ya sa a dace Amin."
Na ce." In sha Allahu zan yi magana da ita.
Ya mike yana duba agogonsa cikin zolaya ya furta." Ni ma a samo mini maganin karfi idan da akwai a Islamic din kwana biyu ba ki gan ni ba kuzari ba."
Ban san lokacin da na wurga masa harara ba, ya fashe da dariya yana fad'in.''Menene to Giwa idan na ce ki nemo mini maganin karfi waye ya fi amfana."
Na tashi ina d'an yin tsaki 'kasa-kasa saboda takaici na ma rasa abinda zan ce masa. Ya riko ni sosai a jikinsa yana yi mini magana a kunne.
Da sauri na dube shi, wai maganar wata haihuwar yake yi mini yana son mai sunan Hajja Halimatussadiya. A ganina idan na sake haihuwa da wannan shekarun kamar zan zama abin kallo yara na yi kai ma kana yi Kamalu da Yusi sun zama zagada zagadan samari.
Ya rike hannuna sosai muka kama hanyar fita daga d'akin yana cigaba da yi mini maganar samun ciki. Wai ana samun mace mai sunan Hajja shikkenan Allah Ya sallame shi. Shiru kawai na yi ban iya ce masa komai ba saboda gudun kada na fad'i abinda zuciyata take gaya mini ya zama lefi tunda shi tsakaninsa da Allah da kuma iya gaskiyarsa yake maganar Allah dai ya kyauta
Sai da na samu nutsuwa tukkuna da yamma na kira anti Yagana a waya muka gaisa sosai tare da tambayar bayan rabuwa ta ce mini Fadila nan tana ta shirye shiryen zuwa domin yi mini kwana biyu na ce ina saurarranta. Daga nan na shiga gaya mata halin da ake ciki da farko ta dinga murna har tana kwarzanta d'abiu da kyawawan halin Sukairaju tunda ya zauna a gidanta shekarun baya da na je bikin babandi garin a lokacin da ya had'a ni da shi domin ya zame masa security lokacin da yake kan sharafin kishinsa. Fadi take yi lallai Hadiza ta yi miji kwarai da gaske abin godiya ga Allah ne. Ban katse ta ba sai da na bari ta gama murna da adduarta tukkuna na gaya mata

matsalar da take damun Hadizan. Jikinta ya yi sanyi sosai cikin kasala da sanyin murya ta furta." Har kin sanya jikina ya mutu Amina wannan matsalar ai babba ce kuma ba zai yiwu a rufe ta ba akan son ranmu amma tasan bata da lafiya mai yasa tun farkon dawowarta ba ta yi magana ba wannan ai rashin hankali ne, domin da ta yi magana tun farko da tuni yanzu an ci karfin magani.
Na ce." Ni ma abinda na ce kenan wallahi anti Yagana Hadiza fa sai da na yi da gaske sosai amma duk ta susuce wallahi idan tana yin wasu abubuwan sai ki dauka ta samu matsalar kwakwalwa."
Ta ce." Dole hakan na iya faruwa domin can inda ta zauna din wani darasi ta koyo mai zaman kansa gida ne da idan Allah ya sa mutum ya shiga a sa'a yake fitowa da raunin zuciya da jin tsoro tare da nadama. Idan kuma mutum bai shiga a sa'a ba sai ki ga ya fito da bushewar zuciya tare da koyo wasu dabi'un marasa kyau wanda suka fi na da muni! Mu dai godiyar da za mu yi wa Allah yadda ta fito da kyawawan halaye."
Na ce." Hakane yanzu dai mun yi magana da maigidan ya ce a nema mata magani ko na asibiti ko na hausa zai saya."
Ta ce." Ubangiji Allah Ya saka masa da alheri ki yi masa godiya sosai mun gode Allah Ya jikan mahaifa."
Na ce." In sha Allahu zan sanar masa bayan kwanaki biyu duk yadda ake ciki zan sanar dake in Allah Ya yarda."
Muna yin sallama na kira GARKUWAR MATA. ita ce mai maganin da na tabbatar da inganci da sahihancinsa duk eanda ya san ni da ita ya san ni domin kuwa tunda na fara amfani da magunguñanta ban kuma marmarin amfani da wani wanda ba na ta ba. 08089965176
Duk halin da Hadiza take ciki na gaya mata a take a lokacin ta ce sanyi ne amma bai riga ya girmama ba kuma idan har an dage da magani za ta rabu dashi.
Na ce ta had'a mini mai kyau ta aiko mini dashi har da set din kayan mata irin wanda nake saye. Ta ba ni tabbacin za ta sanya a mota da sassafe. Muka yi sallama cikin amince sannan na duba details dinta na tura mata kudi har da karin dubu goma  akai ta kira ni tana yi mini godiya taga dubu goma ita kuma me nake buk'ata na ce ta sayawa yara sweet domin yadda nake jin dad'in magunguñanta sai nake ganin babu abinda zan bata wanda zan biyata.
To wata'kila shi ma da abin ya yini duk da ba girkina ba ne da daddare da ya shigo yi mini sallama sai da ya sake tuntubata ya muka yi da mai magani har yana gaya mini anti Yagana ta kira shi a waya tana yi masa godiya. Na ce eh na gaya mata halin da ake ciki ne, mai magani kuma mun gama magana da ita ya ce nawa ne kudin. Shiru na yi ban iya bashi amsa ba sai nake ganin da kunya ace na bari ya biya tunda ina da halin biya shima ya san haka yau da asibiti ne babu yadda zan yi tunda likitocin da suke duba mu shi yake sallamarsu. Ya dinga tambayata na share shi har abin ya bashi haushi ya shiga fad'a na ce." Kudin fa ba su da yawa ka bar shi na biya gobe za ta aiko da shi."

"Tunda dai na ce a gaya mini ai sai a gaya mini komai k'ankatarsu ai ni na yi niyya ko ke ki ka sanya ni ne da zan ta yi miki magana kina ji ki yi banza da ni."
Na ce." Allah Ya ba ka ha'kuri dubu hamsin ne."
Ya gyad'a kansa ba tare da ya sake cewa komai ba ya d'auki wayarsa ya kunna sai kuma ya sake dubana cikin had'e gira ya ce." Na 'karfin mazan fa? tunda duk inda aka samu maganin sanyi ko na basir ba za a rasa na maza dana mata ba."
Na ce." Yanzu fisabillahi sai na ce mata mijina yana son maganin karfin maza ai sai ta raina ni wane irin kallo kake so ta yi maka ko a jikin jarida da kafafan sadarwa idan ta ga hotonka za ta tuna ashe lusari ne na taba saya maka maganin k'arfin maza a wurinta ba zan iya ba."
Ya dinga dariya yana kallona kafin ya tsagaita still idonsa na tsaye a kaina ya ce." To menene abinda ba ni kad'ai ba ne muna nan da yawa a gari fa, gwara ni ma akan wasu."
"Ni dai mijina gwarzo ne tunda har ya iya bada biyu sau biyu a jera aikuwa ba shi buk'atar wani maganin mazantaka gaskiya ba ka yi wannan lalacewar ba tukkuna ai baka wani tsufa  ba."
Ya lumshe idonsa ya bud'e tare da k'ankance su a hankali ya ce.'' Ba ki ji an ce idan da kyau a kara da wanka ba Giwa, ai ba ni nake bada bibbiyu ba Allah ne da damar a hannuna take da tuni na sallami Hauwa itama na bata nata biyun ko na huta da mita."
Ta'be bakina na yi ban ce komai ba domin ba ni so idan muna magana yana yi mini maganarta tunda yanzu sun samu daidaito a tsakaninsu shikkenan kowa ya yi zamansa amma bai fahimci hakan ba sau tari idan muna magana sai ya kira sunanta a ciki. Ganin yadda na kawar da kaina da kallonsa ya sanya shi sauke ajiyar zuciya a hankali ya ce." Kin sanya mini wani shauki da buk'atar kasancewa dake a wannan dare. Kin yaba ni kin kuma nuna bajintata har kina tabbatar da gwarzontakata na tabbatar da cewa har cikin ranki haka maganar take da gaske da za ki ba ni dama a wannan dare da na sake nuna miki jarumtata na kuma roki Allah bisa k'wanjin da zan zage domin raya sunnarsa ya azurta ni da mai sunan mahaifiyata."

na kudi ne littafin kada ki karanta ba tare da kin biyani hakkina ba

A sanyaye na dube shi. da gaske fa yake shi so yake yi na sake haihuwa kuma ciki yake jajibo mini yara ko shekara d'aya ba su cika ba. Yanzu kuma na yi wata magana cibi ya zama k'ari sannan da yake wannan maganar yau da ba girkina ba ne ta hanyar satar kwana za a samu cikin mai sunan mahaifiyar tasa kenan.
Ya ri'ko hannuwana yana dora bakinsa a wuyana yayin da hucin numfashinsa ke sauka a hankali. Tsigar jikina ta shiga tashi na d'an janye daga jikinsa ya kara riko ni a d'an rikice yana bin jikina yana sansanawa kamar muzurun da ya samu nama bayan ya d'auki shekaru bai yi arangama da shi ba.
Na sake janyewa a karo na biyu ina fad'in." Ya kamata ka tafi wata'kila a can idan rabon ya rantse sai ka ga an samu abinda ake muradi tunda ai ka ga ba

zai yiwu ba a cikin hakkin wata ka dinga ikirarin samun mai sunan Hajja idan fa muna neman albarka da kwanciyar hankali.
Ya sake riko ni yana fad'in." Hakan ba haramun ba ne Amina, ki dan ba ni dama mana a cikin wani yanayi nake kwarai da gaske duk da kin nuna ba ki son maganar Hauwa ya kamata ki lura da yanayina ba ni da wata nutsuwa a ranakun girkinta ina kwanciya da ita ne domin hakkinta amma abinda ba ki sani ba shine ba ni gamsuwa irin yadda nake buk'ata. kuma ban fad'i maki haka don na tozartata ba ke ma kada ki yi mata kallon wadda ta gaza a wurin miji Amina ba ni tunanin ko budurwa na kawo ta wadatu da baiwa tare da tarin ni'imar da Allah ya yi miki kin fita daban a cikin mata koyaushe ina alfahari da wannan kyauta da Ubangiji ya yi mini."
Jikina ya mutu sosai to ko dai ya yi ne domin ya ja hankalina tabbas ya samu nasara domin kuwa jikina lakwas ya yi kwakwalwata na tariyo mini zafafan kalaman da ya furzar da su a yau a kaina duk da shi din namiji ne mara k'waron baki ko a shimfid'a ne idan yana nisha'dantuwa ya kan rasa inda zai tsoma rayuwarsa kalaman soyayya da yabawa ina shansu masu tafe da sheshaka da kuma gurnani mai tafe da d'igar hawaye.
Na kan ajiye wannan akan shau'ki tunda ni ma ina yi a wasu lukutan ni da shi din sakarkaru muke zama amma na yau sun sagar mini da gwiwa jikina ya mutu murus ya samu damar tatta'ba ni son ransa amma ban bari lamarin ya wanzu ba domin sai zuciyata take gaya mini idan har kun yi sunna Amina Allah Ya bada rabo to zai iya jarrabarku ta wata sigar domin hakki kuka take babu ruwanki da abinda yake faruwa a tsakaninsu idan yana gamsuwa da ita ba matsalarki ba ce haka zalika ma idan baya gamsuwa da ita.
Na k'wace da k'yar sai kace wasu k'ananun yara ni da shi yana kamo ni ina dojewa na samu na sauka 'kasa cike da mutuwar jiki da tunanin wannan lamari.
Washe gari da safe kalau ya shigo kamar wani abu bai faru ba a tsakaninmu na dinga tunanin yanayin da na bar shi a jiya amma kuma a wartseke ya shigo babu kasala ko k'ankancewar ido gashi kuma da bakinsa ya furta baya gamsuwa irin yadda yake so da Hauwa hakan ya nuna maleji yake yi.
Bai yarda ya amsa gaisuwata a falon k'asa ba sai ya haye sama Hakan ya nuna mini yana buk'atar na bayansa. Ban kawo cewa ga dalili ba ko bayan da na bi bayan nasa gaisawa kawai muka yi ya ce ga abinda ya shigo dashi tunda Allah Ya sa gari ya waye to ya dawo hannuna
Wallahi ni abin ma dariya ya ba ni na zauna ina ta yi ina kallonsa a yadda tun farko muke ai bai dawo hannun nawa ba tukkuna sai da yamma dare ya shiga sai ya shigo na bashi baccin dare daga nan kuma komai ya faru. Yanzu saboda da rigima ya dage yana fad'in kwana biyunta sun k'are har dariyar da nake yi ta bashi haushi ya fara fad'a yana cewa na mayar da shi wawa kenan yana magana akan hakkinsa ina yi masa dariya saboda rashin tausayi.
Ni dai sauka k'asa kawai na yi na kyale shi. Amma daga zarar abin ya fado mini zan yi murmushi ikon Allah. Baccin dole ya yi daya saura na rana na sake haurawa saman saboda lokacin sallah ya yi na same shi ya tashi daga baccin yana ko'karin sauka daga bed din ko kallona bai yi ba ya tashi ya nufi toilet..

Aikuwa dai a daran na gayawa 'yan garin mu abinda duk fitinarsa baya wuce yi sau biyu yau kam uku ya yi yana ta ko'karin yin na hud'u na rasa inda zan tsumbula rayuwata domin kuwa da gayya yake yi yana fad'in tunda ke uwar mata ce bai kamata a ji tausayinki ba. Na galabaita sosai na dinga gwada 'karfina domin na zame amma ina duk ya taushe mini jiki ko'ina na jikinsa 'kwarin gaske k'yam-k'yam! Ya sossoke ni da k'ashin hannu da gwiwarsa.
Da gari ya waye na dinga galla masa harara yana ta murmushi na ce." Ba maganin k'arfin maza ne ya dace da kai ba zumar ki'ba zan saya maka ka yi zuciya don girman Allah ka yi ki'ba kai ko irin tumbin nan na masu kudi ma baka da shi Allah Ya saka mini."
Duk ciccijewar da yake yi sai da ya fashe da dariya ya kishingida lafiyar lau ya ce." Ai na gaya miki irin wannan hawan zan dinga yi miki abinda ba yarinya ba ce ke, giwa wai har kece me yi mini dariya saboda kin raina ni, namiji nake har yanzu."
Na girgiza kaina ban ce komai ba na kama hanya na fita daga d'akin yanzu lamarinsa ya daina ba ni mamaki tunda kullum sabon darasi nake d'auka a wajensa.......✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*171*
To 'kasa da kwanaki goma  Hauwa ta fara amfani da maganin infection din Islamic din GARKUWAR MATA kyakykyawan result ya fito domin da bakinta take gaya mini wurin da ya kumbura ya sa'be sannan ruwan da yake fita yana b'ata mata pant da karni karni da wari shi ma ya daina zuba tana dariya sosai take jaddada mini cewa a matsanancin buk'ace take tun lokacin da ta fara amfani da maganin take matse-matsen cinya sha'awar da ta mance ya ake jin ta shekara da shekaru to yanzu itace take bijiro mata. Lamarin ya ba ni dariya sosai da mamaki lallai na yarda da maganar GARKUWAR MATA da tun farkon had'uwarmu take gaya mini cewa babu buk'atar rantsuwa akan duk abinda take sayarwa ni zahiri ce kwarai da gaske gashi yanzu na sake gazgatawa maganin ne ya wanko mata duk dattin mara har ta fara jin sha'awar d'a namiji tunda gashi da bakinta tana fad'in cewa ta mance ma yadda ake jin feeling din sai yanzu da tasirin maganin ya tasirantu a gangan jikinta.
Aikuwa sai ta zama abar tsokanata bini bini da abin ya fado mini sai nasa dariya ina kallonta har dai ta tsargu ta fara kame-kame tana sake jadadda mini da gaske take yi kuma ba ta fad'i domin na yi mata dariya ba tsabar farinciki ne ya sanya ta kasa rufe bakinta. Ni kuwa na ce ai dariya kam yanzu na fara tunda har lafiya ta samu to auren zai tabbata da izinin Allah.

Ban sanar da maigidan ba sai da ta gama shan maganin na tsayin sati uku tukkuna lokacin ta kara kasantuwa cikin jazaba irin ta buk'atar ruhi da gangar jiki kuma ba ta jin kunyar gaya mini yanayin da take ciki ba.
Ranar da girki ya dawo hannuna bayan mun nutsu ni da shi na gaya masa halin da ake ciki. Ya yi murna sosai yana fad'in abu na gaba a tsakaninsu zuwa yin gwaje-gwaje kamar yadda zamani ya zo da shi domin samun nutsuwa da kwanciyar hankali.
Ni ma hankalina zai fi nutsuwa da yin hakan daga kowane bangare a samu daidaito.
Alhamdulillahi kowane irin tes an yi kuma sakamako mai kyau ya fito na genotype ya yi mini dadi sosai Hauwa AS Sukairaju A-A  Bangaran blood group ma komai ya daidaita yadda ake so. Tsakanin shi da ita sai na rasa wanene ya fi farinciki kasancewar yanzu na taka tudu biyu sai girman da yake ba ni ya kara tsananta duk da maigidan ya gaya masa yayata ce amma risina mini yake yi kuma ba shi yarda mu had'a ido. Ni dai da muka dawo daga asibitin a mota na bar su shi da ita suna zantawa.
Ina shiga ciki na riski Hauwa tare da Mairo a falo suna hira yaran dama sun tafi skull tun safe.
Na zauna kan kujera cikin hijabi don ban iya cire shi ba ganinta a falon a zaune sai nake tambayar zuciyata dalilin zuwanta.
Muka gaisa sosai da sakakkiyar fuska abin har ya so ya ba ni mamaki amma dai na share ban nuna mata na ji dadin zuwanta ba haka zalika kuma ban nuna mata na ji haushin ganinta ba ta ce mini sallama ta shigo ta yi mini farkon wataran maulid wanda saura kwanaki uku kacal mu shiga za ta tafi umara kasa mai tsarki. Na taya murna sosai da fatan alheri mu kad'an ta'ba hirar yara kad'an kafin ta tashi da zumar tafiya ni ma na mi'ke har bakin kofa na taka mata ta fita tukkuna na dawo falon na ce da Mairo ta shiga kicin ta cewa Baba Tabawa su dafa zogalen nan da Masa'udu ya kawo mana tsaraba daga garinsu domin kafin maigidan ya fita ya ce  a yi masa kwadonsa idan ya dawo da yamma zai ci.
Ta tashi da azama kuwa ta nufi kicin goye da Hassan a bayanta. Usaini kuma ina da tabbacin yana bayan Taburni tunda kusan tare suke rainon su biyu wasu lukutan Hadiza da Baba Tabawa na sanya musu hannu.
Hadiza ta shigo cikin annashuwa sai na fashe da dariya ina kallonta cikin zolaya na ce." Masoya masu kafasiti Hadiza na fahimci Sukairaju ya saye zuciyarki kina sonsa ba."
Ta zauna tana kallona da murmushinta har yanzu ta ce." Sosai kam, kin san lokacin kuruciya sakarci muka dinga yi na zo na za'bi mugun mutumin nan Alhaji Halilu Umma da Baba Sule  suka rud'e saboda watsi da kudin da yake mini, lokacin wallahi ban san menene so ba Amina ni ma kudi da jin dad'in kawai nake hange ashe mugu ne azzalimi na ci wahala a hannunsa ba kad'an ba."
Na gyada kaina a tsanake na ce." Kaddara ce ai Allah ya zano shi a matsayin mijin da za ki aura amma shawara anan shine kada ki yarda ki nuna masa tsananin son da kike yi masa maza suna da wani abu a duk lokacin da suka gane mace na mutuwar sonsu to sukan kwatanta rashin adalci a kanta.

Amma ba duka ne suke da wannan halin ba. Ban ce kada ki nuna masa k'auna ba amma daidai misali."
Ya gyad'a kanta a hankali tana fad'in." In sha Allahu zan lura amma fa ni kaina yanzu ne nake jin ina soyayya Amina."
Na yi shiru ban ce komai ba sai ta cigaba da cewa yanzu muka gaisa da Hauwa a farfajiya ta tare ni da fara'a sosai abin har ya ba ni mamaki."
Na ce." Ta sauko ai tana neman shiri ta zo yi mini sallama ne wai za ta tafi umara cikin satin nan."
Ta ce." Allah Ya kar'bi ibada ya sa ta je lafiya ta kuma dawo lafiya."
Na amsa da Amin ta d'an yi jim kafin ta cigaba da cewa." Wai tambayata take yi yaushe zan je gidanta mu gaisa sai na ce mata zan zo in sha Allahu. Shine ta wuce tana cewa wai tana saurarena kafin ta tafi umara."
Na ce." Wata gaisuwar kuma za ku yi bayan wadda kuka yi a yau Hadiza?"
Ta ta'be bakinta tana fad'in." To ni ma haka na gani sabon salon makirci ne ai babu inda zan je kuma ni ban yarda da wannan faram-faram din na ta ba, hausawa suka ce  ruwan da ya dake ka shine ruwa.
Ban ce komai sai murmushi na saman lebe Hauwa kenan neman mutane take yi yanzu ga shi kuma ba ta iya mu'amula ba. Nusaiba ta sha gaya mini wai tana kiranta a waya ita har tana mamakin a ina ta samun lambarta yarinyar da ta yi wa zagin tsamar nama da cin zarafi shine yanzu take janta a jiki saboda tana kishin yadda yaran ke dabdala a gidana domin ko zuwan Salim hutu nan wurina yake d'aukar abinci kamar yadda d'an uwansa ke zuwa ya d'auki na rana da daddare Adam kwana ne kawai ba ma yi a tare a gidan. A can gidansu yake kwana tun bayan abinda ya faru da Nabila to yanzu kuma sun juya Legos din shi da Salim din domin cigaba da gudanar da abinda zai kawo musu cigaba a rayuwarsu. Lamarin yana yi mata zafi ba tun yau ba na lura da cewa ta tsani duk wanda zai ra'be ni shima sai ta dasa masa k'iyayya. To yanzu kuma taga hakan bai yi ba ta fito da wani salon. Lambar waya ai ba za ta yi mata wahala ba ko a wurin mijinta za ta iya samu.
Kafin ya shigo gidan ya kira ni a waya yana fad'in zogalan nan da Masa'udu ya kawo dama buhu guda ne d'anye sai uwar doya da albasa ya ce a dibarwa Hauwa na ce to ina mamaki shin shine ya gaya mata ko kuwa a takaice dai na ce." Zogalan kad'ai ka gaya mata an kawo ko da sauran abubuwan?''
Na ji shi yana fad'in.'" Shi tace tana buk'ata idan ma aka ajiye shi zai bushe ko ya lalace ku d'ibar mata tunda tace tana buk'ata."
Na ce." Ba wani lalacewa da zai yi ai kana son miyar zogale sai mu busar da shi."
Ya ce." A d'ibar mata dai na ce." Sai na tare shi da sauri ina fad'in." Ai shine na ce iya zogalan kawai ka gaya mata an kawo ko da sauran tsarabar."
Ya ce." A a ni ban gaya mata ba Giwa mun yi waya ne yanzu take gaya mini ta shigo yi miki sallama bayan ta fita suka gaisa da Masa'udu tasan ya yi tafiya zuwa garinsu shine ya gaya mata abinda ya kawo muku."
Na ce." To tunda hakkinta za ta fitar mata  ai kamata ya yi ta buk'aci sauran kuma saboda neman magana ni me yasa ba zata gaya mini ba."

Cikin k'osawa ya furta." Ba ni son 'karamar magana ta zama babba Amina kwana biyu abubuwa sun yi sanyi dalili na fahimci kowacce a tsakaninku kada ki girmama lamarin don ta sanar da ni ba wani abu ba ne, ni kuma ai gashi na gaya miki."

Na ce." Munafurci ne kawai idan da yarda babu wani nufi a zuciyarta ai ni ya kamata ta gayawa tana buk'ata tunda tana da lambar wayata."

Ya datse kiran ba tare da ya ba ni amsa ba.

Kicin din na shiga na ce su raba tsarabar nan kashi biyu daidai a bawa Hauwa.

Hadiza dake gyara alayyahu ta ce." A a ai nan kuke da yawa Amina na yi zaman gidan iyali na gani kin san dai Alhaji Halilu matansa biyu ni ce ta uku ko, to duk abinda ya kawo nawa ne kad'an tunda ba ni da yara. Me zai sanya za a yi haka kuma?"

Ina dariya na ce." To Masa'udu garin kaud'insa ya gaya mata ya kawo tsarabar zogale da albasa tare da doya shine tana zuwa gida ta kira maigidan wai tana son zogale.

Taburni ta ce ." Ban da abin Hajiya Hauwa ai ke da ita duk daya ne sai ta gaya miki tana buk'ata ta shigo ta dibi yadda ranta yake so."

Murmushi kawai na yi ban sake tankawa ba Ina jin su suna ta magana. Hadiza na fad'in." Idan an raba an bata biyu ba a yi miki adalci ba."

Anan ne na ce to wannan tsaraba dai ta Masa'udu na neman ta janyo cecekuce ayi dai yadda na ce din idan ma kyautar da su za ta yi shikkenan a bata zogale ne dama yake yi mana wahala don ta doya da albasa wannan ai ba matsalarmu ba ce ko ku raba daidai a had'a mata cikin buhu sai ta aiko ta d'auka."

Na juya na fita daga kicin ina jin maganganunsa akan lamarin.

Yana kuwa shigowa da abinda ya fara kenan na ce an raba kashi biyu ta aiko ta d'auka ko kai ka d'auka ka kai mata.

Yadda na fadi maganar a harzuke shine abinda ya sanya shi tsirawa fuskata ido yadda ya nuna kamar abin ba na tashin hankali ba ne gashi ina ko'karin girmama shi. Ni abinda ya ba ni haushi yadda ta kasa tambayata sai shi zata tambayata tunda ai Masa'udu direbansa kuma shi ya kawo kayan babu buk'atar ta tambayeni wanda yake zaune dominsa shi za ta tambayata ni ban isa ba. Yanayin yadda ya damu da lallai sai an bata tamkar wadda ta bawa umarni.

Haka dai ya dinga kaucewa neman fitinata domin so na yi ya tanka na fad'i abinda yake raina sai ya'ki biye mini ya kira ta a gabana yana fad'in ta turo Ladidi ko yaron dake bawa shokokin gidanta ruwa ya d'aukar mata.

Ya kashe wayarsa. Ya dinga jana da hira a lokacin da nake zaune a gefansa yana aiki a computer na ki biye masa ni ma. Sai ya ja bakinsa ya yi shiru tsayin minti ashirin da biyar ya gama abinda zai yi ya rufe Loptop din Yana kallona ya ce." In banda dole sai an janyo mini tsiya a gidana ya za a yi rigima akan zogale Amina wai don Allah menene yake damunku ne?"

Na dube shi ina fad'in." Halin tsiya ai yana wajanta Allah Ya yi maka mai kyau duniya da lahira ni ai ban ce komai ba, ka ce a dibar mata zogale an yi yadda ka ce din to kuma sai ya zama lefi."

Ya gyad'a kansa still idonsa a tsaye a kaina ya furta." Shine na ce ai kuna nema ku ba ni kunya saboda rashin tsinkaye da tunani ita tana can tana surutai na banza bisa wani zargin da bashi da toshe ke kuma gaki ba ki da fahimta wato cewar da na yi a dibar mata zogalen da Masa'udu ya kawo sai ya zama a lefi a wurinki Amina har ki dinga ko'karin zagi na."
Da sauri na ce." Yaushe na zage ka don Allah?"
Ya nuna kirjinsa da yatsa yana fad'in." Kin san dai ba zan yi miki k'arya ba ko, ai ni ba kurma ba ne na ji lokacin."
Kasa'ke kawai na yi ina kallonsa da mamakin yaushe ya koyi 'karya mai lasisi irin haka. Nasan dai gwani ne shi wurin juya magana idan yana so ya kare kansa ko ya kashe wata rigima yanzu nan zai sar'kafe ya cukurkud'a magana ya kuma dage shine da gaskiya yanzu ma abinda ya shirya yi kenan uana so ya d'aure ni da jijiyar jikina ban zage shi ba amma gashi yana fad'in na zage shi ai ba mahaukaciya ba ce ni.
Ya cigaba da sakin maganganu." Duka kun raina ni wallahi saboda na yi sanyi ina bin kan kowacce da abinda take so babu wadda nake tsoro na yi miki ta bafulatani aradu na d'aga 'kafa ne kawai don ganin yarana suna girma nan da shekaru takwas twins dina sun zama cikakkun 'yan mata 'yan 16years lokacin ko ina raye ko ba na raye Allah ne ka'dai masani."
Ya sassauta maganar cikin alhini tare da 'kura mini ido.
"Hum kawai na ce kafin ajiyar zuciya ta biyo baya na furta." Allah Ya kyauta dai Ina ganin dai ko tsufa muka yi gaskiya da wahala matarka ta canza domin ko kai kasan yadda nake hakuri bisa dabi'unta yanzu don girman Allah menene don ta kira ni ta ce tana son zogale kai ba ka yi tunanin cewa akwai wani abu a zuciyarta ba har yanzu."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Yadda ba zata canza ba haka zalika kema ba za ki janza ba giwa. Na san halin kowacce a cikinku. tunda Ubangiji na ya jarrabeni daku a matsayin abokanan rayuwa dole na yi hakuri mussaman kuma da kuke ha'kuri da ni."
"To yanzu dai idan na fahimta ka goyu da bayan abinda ta yi kenan tunda na ga kamar kana kare ta."
"Ban goyu da bayanta ba Amina na nuna mata cewa tana da ikon shiga kicin dinki ko kuma ta tambayeki ba ni son kumbiya-kumbiya fa wasu lukutan daga cikin dabi'unki na burge ni domin ba ki da rufi kuma ba ki da munafurci na gane shine dalilin da ya sanya idan an yi miki hakan yake yi miki zafi."
Na janye idona daga kansa ba tare da na ce komai ba. Ya saki ajiyar zuciya yana fad'in." Kafin na shigo Sukairaju ya yi mini bayani har results din duka ya nuna mini. Na yi murna na kuma yi addu'a kwarai abinda za a yi yanzu da kaina zan tashi zuwa Kano wajan Baba domin nemo auran hakan ya yi ko?"
Na d'an saki fuskata ganin yadda ya karrama ubana har yana kiransa da Baba na ce hakan ya yi sosai Allah Ya tabbatar da alheri."
Ya amsa da Amin yana fad'in." Idan kuna da idon sanin can garin nasu Sukairaju hakkinku ne domin fad'ad'a bincike a kansa da zuriarsu domin sake gazgata abinda muke hasashe da wanda na sani a kansa."

"Gaskiya ba mu da kowa a garin wallahi, amma komai na Allah ne kuma tunda ka ba da tabbacin akansa da zuriarsu ai ba sai an sake wani binciken ba alheri dai muke ta addu'a akan Allah Ya wanzar musu damu gabad'aya.''
Ya ce." To hakan ya yi in sha Allahu rabbi cikin satin nan zan shirya zuwa Kano kuma babu buk'atar d'aukar dogon lokaci tunda dukkaninsu babu yaro a ciki."

***

To idan Ubangiji na ikonsa babu wani mahaluki da duk iko da shahararsa a duniya da ya isa ya dakatar buwayar Allah domin kuwa rahamominsa suna da yawa. Ni dai ban taba tunanin wai akwai dangantaka ta aure tsakanin Hadiza da Sukairaju ba sai yanzu da Allah ya bankad'a abinda yake rubuce a kudirarsa. Kamar yadda nake wannan tunani da mamakin itama nasan haka take cikin wannan tunanin na kasantuwar auransu da Ubangiji Allah yake shirin tabbatarwa.
Bayan zuwansa wajan Babanmu an samu nutsuwa sosai da fahimtar juna tare da amincewa daga kowane bangare domin kuwa ba su riga ma sun tsayar da maganar d'aurin auran ba sai da kawunan Sukairajun suka zo su biyu daga Zamfara aka yi zaman dasu tare da bada sheda da tabbacin cewa sun kar'ba bisa amana. A take a lokacin ya biya sadakin Hadiza bisa jagorancin kar'bar auran da ya biyo ta hannunsa. Hadiza ta yi goshi dubu dari biyar sadaki suka tsayar da ranar d'aurin aure ranar takutaha ranar da aka haifi manzon Allah s.a.w domin samun falala da dacewa.
A ranan da daddare Ummansu ta kira ni a waya godiya kamar za ta yi kuka har sai da na ji wani iri a raina na dinga tausarta domin dai kukan da ta dinga dannewa sai da ta yi shi a cikin waya da kyar muka to sallama. Na kira anti Yagana a gaban Hadizan na sanar mata da yadda aka yi itama murna kamar ta zuba ruwa a k'asa tasha. Hadiza na gefe sai murmushi take yi domin tunda na gaya mata mun yi waya da maigidan ga yadda ake ciki ta rasa yadda za ta yi da ranta saboda farinciki.
Kwanansa hud'u a kano ya dawo da daddare tare suka je da angon dama. Na tarbe shi sosai tare da yi masa bangajiya da godiya a daran kuwa ya samu tar'ba mai kyau mai tafe da sabon salo wanda bai san shi ba.
Muka shirya tafiya kano kafin zuwan ranar ni da ita da yaran duka tunda an yi musu hutun boko da islamiyya mun shirya walima domin nuna farincikinmu ga Allah anti Yagana ma tana can tana shiri domin ta ce kaf yaranta da su zata zo.
Saura kwana biyu mu tafi Hamusu ya kira ni yana gaya mini Sukairaju ya sanya shi had'a lefe akwati shida tambayata yake yi aure zai yi?"
Hadizan tana zaune a gefena a lokacin da muke yin wayar na gaya masa aure zai yi kuma Hadizar gidanmu ya kuwa shiga farinciki sosai yana ta fad'in ta samu lefe domin milayan shida ya tura ya ce a had'a lefe na kece raini kuma a shagonmu." Lamarin ya yi mini dadi sosai na juya ina kallonta tana murmushi bayan mun yi sallama da shi na dube ta kafin ma na yi magana ta furta." Kudin ya ce zai ba ni sai kawai na ce ya yi magana da Hamusu ya kuma tura masa shi zai had'a komai."

Da murmushi a tare da ni na furta." Na taya ki murna Hadizan gidanmu ta yi goshi kin zama bazawara mai kafasiti yanzu abinda ya rage muna dira kano a yi gyaran jiki sannan na kai ki gidan GARKUWAR MATA ta had'a mini ke da kyau!
Ta kuwa fashe da dariya sai ka ce wata shashasha.  Na shiga taya ta sai muka zama kamar sakarkaru rayuwa kenan bayan wucewar kalubale mababambamta da 'kin jinin juna tare da 'kyama ashe akwai ranar da Hadiza za ta k'aunaci cigabana duk son kud'inta sai ta ce a a gwara a yi sayayya a wurina saboda na cigaba. Lallai bahaushe ya yi gaskiya da yake fadin ranar naka sai naka............✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124....BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*172*
Duk abinda ya kamaci Hadiza na gyaran jiki ni na d'auki nauyi don har tana cewa za ta gayawa angon ya bata kudin gyaran jikin na ce a a kada lalacewar ta yi yawa yadda ya fitar da kudi masu kauri domin yi mata lefe irin na budurwa mai jini a jika bai kamata a ce ya bada wasu kudin ba. Sosai na yaba masa dangane da abinda ya yi mata duk a kokarinsa na ganin ya dakusar mata da damuwa kuma da alama yadda Allah Ya jarrabeta da sonsa haka shima yake k'aunarta domin matar so ai ake yi wannan hidimar a matsayin dai Sukairaju tsayayyan namiji mai suffa da mazantaka ina da tabbacin ba zai rasa 'yan mata da suke kawo masa caffa ba. Amma shi so babu ruwansa Hadiza ya hango cikin dubbanin 'yan mata da zawarawan da suke a wannan duniya.
Anti Yagana ta riga mu zuwa domin da muka isa kanon  a gidana na sharad'a muka sauka sannan gari yana wayewa muka yi gidan GARKUWAR MATA yini muka yi a tare da ita ta sabunta ni ta kuma sabunta Hadiza da ciccibi tare da dahuwar 'yan shilla aure biyu da duk wani abinda ya kamata.
Kuma Koda muka gama da ita gidana muka sake komawa sai da gari ya waye bayan mun kintsa muka nufi can gidan na mu gabad'aya ni da ita da Baba Tabawa domin tare muka zo da ita saboda yaran Mairo da Taburni suna gida Abuja muka bar su.
Gidan an yi masa sabon fenti ciki da waje har da ties a tsakargidan da d'akunansu wannan aikin Usaini ne ya gyara gidan sosai bayan wanda na yi musu ya yi musu sabbin d'inkuna Babanmu tsaf da shi cikin manyan kaya ya sake murmurewa. Sosai hankalina ya kwanta ganin yadda aka samu daidaito tsakanin matan gidan duka sun daina abinda suke yi Ummansu Saminu ta fito ana ta hidima da ita yayin da 'yan uwan Ummansu Hadiza suka cika gidan zuwa na ya sake bud'e babin gaisuwa har da rige-rige a tsakaninsu lamarin nan dai ya tabbata da ake cewa kudi suna sayan girma kuma suna kankaro mutunci. Ma'kotan gidanmu da ada suke yin surutu a kaina a duk

lokacin da Ummansu Hadiza ta yi musu gulmata sai na zama abar fadanci da gurfana tamkar wata basarakiya.
Ranar da aka d'aura auran da daddare ya kira ni yana gaya mini bai tafi ba sai gobe don haka Ayuba zai zo ya d'auke ni da yaran mu kwana can gidana na sharad'a.
Na ce masa ya bari gari ya waye domin duk mun gaji har yaran su Hassan ma sun yi bacci tun d'azu. Ya ce a a mu Ayuba zai zo. Haka na kintsa ina gayawa anti Yagana yadda muka yi da shi ta ce mu tafi din kawai tunda hakan ya bukata.
Wajan tara da arba'in Ayuba ya zo ya kwashe mu a mota amma banda amaryar tukkuna dole za ta yi sallama sosai da mahaifiyarta.
Kwanciyar aure zai yi da ni a daran ashe shine dalilin da ya matsanta lallai sai mun dawo dalili matar da yake d'an ragewa da ita tana can saudia basu dawo ba shi ya gaya mini tare ya biya musu da mahaifiyarta da kuma Kawunta da ya zo ya yi musu sulhu wattanin baya. Daga lokacin na gane dalilin da ya sanya ta sassauto har take taka kyasa da k'arfi ganin ta fara samun kansa kyautar umara ya yi wa iyayenta biyu wannan kuma shine karo na biyu tsakaninta da Inna Uwanin a shekarun baya tun kafin ya kai k'arfin haka ya ba su kujerar ita da Hajja da Samira duk su hudun suka je lokacin suna soyayya kafin auransu.
Ya yi yadda yake so ban hana shi ba dalili nasan ya jure tunda kusan kwanaki biyar kenan rabon da mu had'u da safe yake gaya mini gidan da ya mallakawa Sukairaju amma ba a cikin estate din da muke ba ya d'an yi gaba da mu. Ya nuna mini shi a waya maidaidaci ne plate wanda aka yi wa ginin zamani daidai gwargwado kuma ya ja kudi sabo ne kuma na yi masa murna sosai ya kuma tabbatar mini da cewa a shirye gidan yake shiga kawai za su yi.
Yini guda muka yi da shi a d'aki yana ta maimaita abu daya don a k'alla sai da ya neme ni sau uku bayan wayewar gari da safe bayan mun karya da azuhur ya yi sallah sai kuma da yamma wanda shi ya yi bala'in gabalabaitar da ni na yi kwance a gado ina nishi wai lallai sai an samu ciki bayan shi kansa ya san yawan yin wannan abu ba shine yake bada ciki ba. K'addara ma a samu d'in amma ai ba mu da hurumin nunawa Allah abinda muke so idonsa gabad'aya ya rufe har na rasa inda tunaninsa yake har da cewa yana ganin a shekarar nan zai mutu shiyasa ya damu da ganin na sake haihuwa.
Baba Tabawa ita ta dinga hidima da yaran gabad'aya domin ban sauko ba sai bayan biyar da rabi a gajiya tubis ga gajiyar bikin Hadiza ga wadda ya tara mini
Ta yi abinci tsaf ta gama shirya ko'ina da yaran gabad'aya suna zaune a falo suna kallon cartoon  Hasan na wasa a kusa da ita shi kuma Usaini na dafa kujera yana mi'kewa tsaye Sultan na ri'ke hannunsa.
Na zauna cikinsu zamana kuwa ke da wuya suka rufe ni kowa da abinda yake fad'i mussaman Minal duk ta kanainaye ni ta ko'ina.
Yana dawowa daga sallar magriba yake gaya mini rasuwar Malam D'aha a lokacin ne Malam Rabi'u abokinsa ya kira shi a waya ya sanar da shi amai da gudawa ya yi kwana daya don asibitin zana ya rasu.

Na kadu sosai da rasuwar malamin jikina ya mutu na zauna ina Kiran Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un babu babu shakka maza sun tafi Allah Ya kar'bi ayyukan alherin da aka yi dominsa.
Da sassafe mu ka dauki hanya ni da shi domin samun ta'aziyya a daran dama na kira Usaini na ce cikin hikima ya san yadda zai sanar da Hajara domin kuwa tsohon ciki ne da ita haihuwa ko yau ko gobe ya tabbatar mini da cewa da wuri za su tafi shi da ita inshallah.
Aikuwa a can muka same su gidan Malam ya kacame unguwar ma gabad'aya motocin manyan mutane ta ko'ina da yake karkara ce akwai filaye sosai da aka samu damar ajiye motacin.
Hajja ma can muka same ta lokacin an gama shirya gawar za a fito da ita domin a sallace ta.
Sai bayan da aka d'auke shi zuwa gidan sa na gaskiya tukkuna na samu sararin bin dakunan matan gidan ina yi musu gaisuwa da yaransa mata aurarru Hajara na cikinsu sun yi kuka har sun gaji na yi musu gaisuwa sosai kafin na koma na zauna wurin da Hajja take a killace muka sake gaisuwa tare da yi wa juna ta'aziyya. Wajan biyu na rana Babanmu anti Yagana Hadiza da su Fati da Ummansu Saminu suka zo Ummansu Hadiza kawai a ka bari a gidan Saminu da Ashiru duka tare suke Hajara da kanta ta dinga bi da su d'akuna suna yin ta'aziyya sannan mazan suka fita waje su kuma su anti Yagana muka zauna a tare a wuri d'aya.
Hajja can muka barta da za mu tafi ta ce ba zata iya wannan kai kawon ba sai anyi addu'ar uku tukkuna. Amma ni da shi haka muka dinga wannan kai kawon muje  mu dawo har sai da aka yi addu'ar uku tukkuna. Ranar sadakar bakwai kuma shi kadai ya tafi bai ce na shirya ba sai ya dawo tukkuna yake gaya mini tare suka je da Hajja.
Kwanaki goma da rasuwar Malam D'aha muka shirya komawa abuja lokacin Hauwa ta kwana kusan shida da dawowa kira shi a waya babu adadi ya kuma gaya mata babban rashin da aka yi ba wai jin dad'i ne ya zaunar da shi ba don a ganinta tunda muna tare  wata'kila ni na hana shi dawowa bayan kwanakin da ta yi a saudia ya kamata a ce ya yi d'okinta.
Ranar da muka koma kuwa a gidanta ya kwana domin hura masa wuta ta yi babu kintsi ya tafi ba cikin dad'in rai ba.
Hadiza a can muka bar ta. Sai bayan sati daya tukkuna angon ya je ya daukota kai tsaye kuma gidanta ta sauka sai da ta kwana biyu da tarewa tukkuna na je na ga gidan alhamdulillahi Hadiza ta 'yantu ta yi gida gayun nan da ake ta nema yanzu ya samu an ci ado da kwalliya irin na amare abin dai gwanin burgewa da sha'awa nan take gaya mini Ummansu ta ce bayan ta dan yi wattani sai su shirya zuwa ganin d'aki dangin babamu da danginta na ce hakan ya yi Allah Ya sanya alheri.

Kwanaki talatin da uku da rasuwar Malam D'aha Hajara ta haihu mace tun daga haihuwar aka ce mini an yi mini takwara dole haka na shirya tafiya da gudumawar kayan baby kwanaki uku kacal na yi a daddafe domin da 'kyar ma ya bari na dawo gida tunda ba taron suna aka yi ba saboda rasuwar mahaifinta. Amma alhamdulillahi ta haihu lafiya lau ita da baby suna cikin

koshin lafiya yarinya kamar Usaini ya yi kaki ya tofa saboda tsananin kammani.

Na kudi ne littafin kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

****

Bayan wata hud'u zaman namu ni da Hauwa yana ta tafiya a waskace babu tsari sai dai zangon 'kasa da kuma bita da 'kulli tunda nake kafata bata ta'ba taka gidan Nusaiba ba wallahi don wasu lukutan har kunyarta nake ji yarinyar har ta gaji da tambayata yaushe zan zo nakan ce mata ina tafe in sha Allahu amma Hauwa ta riga ni saboda gulma tana cin ko'kon ranta kawai yarinyar ta kira ni a waya tana gaya mini wai Hauwa ta je mata ta yini har ta kai mata mayafai biyu da hijabai irin wanda ta zo da su daga makka har tana gaya mata cewa Hadiza ba tsaran auran Sukairaju ba ce dalili karuwa ce kuma 'yar kungiyar shan jini an cutar da shi kuma ta girme shi nesa ba kusa ba wataran za a wayi gari babu shi ta nemi wani sassa na jikinsa domin alamu sun nuna zaman da ta yi gidan gyaran hali bai koya mata darasi ba don haka dole za ta matsantawa maigidan ya dawo mata da yaranta saboda tana jin tsoro kada a wayi gari babu daya daga ciki mun had'a baki mun bawa dodon tsafi tunda ni kishiyartace kuma ba ni k'aunarta zan iya yin komai domin ganin bayanta da yaranta saboda ni da 'ya'yana mu gaje dukiya.

Wallahi bakina mutuwa ya yi na rasa abinda zan cewa yarinyar kaina ya yi bala'in d'aurewa wata'kila fahimtar hakan ta yi daga wajena yasa ta shiga ba ni ha'kuri tana fad'in ba ta san hankalina zai tashi ba kuma ta yi rantsuwa da Allah ba ta ta'ba gazgata maganarta ba domin ni din ma na fiye mata ita sau dubu.

Har muka yi sallama ban iya ce mata komai ba saboda mamaki lallai wannan al'amari ya daga mini hankalina ba kad'an ba. Duk wasu kaidi da sharri Hauwa ta yi mini na jure saboda dalilai masu yawan gaske amma ina ganin wannan kam ba zan iya ha'kura ba dalilin da ya sanya kenan yana shigowa ban ma bari ya huta ba saboda da abin na yini shima ganina a hargitse cikin rashin nutsuwa ya shiga hankalinsa na shiga gaya masa abinda kunne na ya ji wanda nake da tabbacin cewa yarinyar nan Nusaiba ba za ta yi mini karya ba.

Ya shiga mamaki kwarai shima jikinsa ya yi sanyi mussaman yadda ya ga hankalina ya tashi ina kuma sake jaddada masa cewa shari'a ce zata raba tsakanina da ita idan kuma bai yadda da hakan ba ya zama dole ya za'bi zama da ni ko'ita domin ba za a cigaba da tafiya a haka da ni ba ya zame mini dole na nemi mafita.

Kwanan rarrashi ya yi duk da girkinta ne sai ya kashe wayarsa ma gabad'aya domin kada ta kira shi ya rufe dakin da key ya boye shi saboda kada na fita rarrashina ya dinga yi sosai lamarin na sa'barsa shi kansa yanzu yadda yake nunawa lamarin Hauwa ya kai shi ma'kura akwai dalilan da ya sanya yake daga mata kafa wanda ni ma su nake duba mussaman yaranta Khalil dai

biyayyar da yake yi mini kwatankwancinta ba ta samu ba ga Minal da take jarabar kulafucina uwa uba kuma ina duba Hajja domin duk lalacewarta tata ce idan na yi tutsu abubuwa da yawa marasa dad'i za su faru wanda za su sanya kunci da zubar hawaye a idanuwan yaran.
Wallahi kwana cur ba mu rintsa ba har sai da ya karya mini lagona da rarrashi da kalamai tare kuma da al'kawaruruka da tabbaci akan idan ta sake aikata abu makamamcin wannan da kansa zai d'auki mataki.
Sai da ya yi mata ya ji na sati d'aya bai je gidanta ba ta kuwa zama kamar mahaukaciya ta zo gidana ya fi sau hud'u ba ni ma sanin zuwanta sai dai idan na fito daga d'aki yara ko masu aiki su ce mini ta zo. Shi kuma ba ta ma riskarsa domin yakan fita da wuri kuma baya dawowa sai dare.
A ranar da ya cika sati guda ya koma gidan wanda na tabbatar da cewa wannan ba shine iyakacin horon ba akwai wasu mabambamta yadda ya yi wannan fushin kuma  sai ta gayawa aya za'kinta.

Hakan da ya yi sai ya kara sassauta mini rai amma dai duk haka cikin k'unci da takaicin abin nake don sai da na sanya aka yi mini saukar al'kur'ani can makarantar allonmu dake cikin unguwar mu duka cikinta muka yi sauka al'kur'ani mai girma a duk lokacin da masifa ta tunkaro ni nakan sanya an yi mini sauka da addu'a sannan a yi sadaka Hamusu ne ya jagoranci al'amarin sati guda aka d'auka ana sauke izifi sittin a lokacin na fara jin sanyi a zuciyata. Maigidan ya kuma zo mini da albishirin kammaluwar ginin shagunana har ya nuna mini bidiyon wurin a waya waje ne mai darajar gaske a cikin kasuwar ta wuse market gini ingantacce na zamani mai tafe da 'kawa kamar yadda ya fadi madaidaiciyar plaza ce mai d'auke da shaguna sha biyu masu matsakacin girma kasa da sama ko'ina gwananin sha'awa ga Ac ta kowace kusurwa da manyan panal na solar haske ko ta ina yanzu shawarar yadda za a yi tana hannuna sai abinda na ce haka yake gaya mini yana lankwasar da kai da murya duk a k'okarinsa na ganin ya kashe guguwar wuta mai tartsatsi da take shirin kamawa a gidansa.
Ni kuwa na ce da shi yadda ya bada umarni haka za a yi amma dai ina so na yi amfani da 'bari d'aya sama da k'asa d'aya side d'in a bada shi haya ya ce hakan ya yi.
Bayan kwana biyu ya shigo har d'akina ya same ni ban jima da fitowa daga wanka ba ya dinga bina da kallo har sai da na tsargu na dube shi ya sauke ajiyar zuciya a hankali ya furta." Ciki ki ka samu ne?" Na ji wani bala'in fad'uwar gaba domin kuwa akan ga'ba nake ina sanya ran ganin al'adata cikin kwanaki biyun nan.
Sai na girgiza kaina ina fad'in." A a mai ka gani?" Ya d'ora hannunsa saman kirjina da suke da towonsu har yanzu ba su langa'be ba ya ce na ga sun girma sosai kin d'an yi kumburi Giwa ina fahimta a duk lokacin da ki d'auki ciki kina canzawa fa har yatsunki.
A sanyaye na ce." To wallahi ba zan tabbatar ba amma don Allah ka daina kira mini shi yanzu ka taimaka mini na rantse da Allah na wuce haihuwa Allah Ya raya mana wanda muka samu."

Ya zuba mini ido fuskarsa ta canza da wani yanayi ya furta." Ni ba za ki taimaka mini ba kenan. Na jima ina gaya miki ina son samun uwata Halimatussadiya sai ki ce na tausaya mini indai ni ban wuce haihuwa ba Hajiya kema ba ki wuce ta ba, mu riko Allah Ya ba mu mai albarka na ce ko daga haka sai na godewa Allah."
A sanyaye na ce." Ai shikkenan." Ya rike hannuna yana dan murzawa ya furta." Ki ce Amin kin ji ko Allah Ya sa shi din ne, domin a jikina nake ji hakan!"
Na dube shi ganin yadda ya zura mini idonsa ya sanya na ce ." Amin Allah Ya sa shine."
Ya kuwa sauke ajiyar zuciya yana fad'in." Na gode miki sosai Allah Ya yi albarka."
Na amsa da Amin a takaice kafin ya sake kallona a karon da babu adadi.
"A game da abinda muka sanya a gaba ni dake a yanzu nake so na ji a ina aka kwana ina so mu wuce wannan wurin ne zan je Legos ina da uzuri a can din amma ni kad'ai nake son tafiya."
Na ce." Business din da nake yi cikin garin kano na zannuwa takalma da huluna nake so na kawo shi nan din kamar yadda na gaya maka da farko amma ina so shaguna biyu na zuba supplements ina so na jarraba ana samun alheri."
Ya d'an yi jim kafin ya ce."Supplements kayan gyaran jiki na mata da kwalliya ko?"
Na gyad'a kaina idona a kansa ya ce ." Hakan ya yi Allah Ya ba ki sa'a, amma ba ki sha'awar sayar da kayan maza ina nufin irin wanda muke sanyawa tunda harkar huluna ta kar'be ki sai ki sa hannu anan din domin mu ga abinda Allah zai yi."
Na ce." Hakan kuwa ya yi sosai na gode da shawara Allah Ya saka da alheri zan yi ko nan gaba don ba ni tsammanin abinda yake hannuna a yanzu zai ishe ni yin duk abinda nake buk'ata.
Ya ce." Ni zan yi miki order domin shirya shagunan tunda na bada shawarar yin hakan amma har yanzu ba ki fitar da sunan shops din na'ki ba. Ita kanta plazar akwai buk'atar a samar mata da suna na mussaman ko?"

Nan fa d'aya wallahi na manta shaf kuma dai da kunya na ce masa sauran shagunana  suna d'auke da AminatuAminu collocation ne. Tun lokacin da na fara bud'e shagon d'inki na sanya masa A-A fashion designer hakan na nufin AminatuAminu sai Kuma da na bud'e shaguna tukkuna na bud'a sunan kowa ya gane abinda nake nufi kuma har zuwa yanzu wannan tambarin ne a jikin duka shops dina sai dai a sabunta idan ana so a sake 'kawata lamarin. Ina so a ko'ina ya cigaba da tafiya a haka domin cirewa customer's d'inmu  shakku da kokwanto.......

Masu karatu ku ba mu sunan da ya kamata a kira shop's din Amina na Abuja don Allah kada a yi rashin adalci.......😃
Plazar dai na yi mata suna da (GIWA PLAZA) shin ta cigaba da amfani da AminatuAminu tunda da shi a kasanta.....✍️

*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP #700 VIA 0542382124.....BINTA UMAR GTBANK.*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*173*
Har yanzu idanuwansa na tsaye a kaina jikina ya k'ara yin sanyi kasala ta mamayeni bakina ya mini nauyin da na kasa ce masa ga yadda nake so komai ya tafi daidai da abinda na gina shekara da shekaru ai da kunya da nauyi duk da yanzu babu shi a raye a duniya amma mafiakasari mazan mu na yanzu ba sa rasa abin kishi koda ga wanda ya mutu ne mussaman da na riga na fi kowa sanin halinsa mutum ne shi mai zazzafan kishin tsiya. Kawai sai na tsinkayi maganarsa yana fad'in." Za mu cigaba da kiran shops din da AminatuAminu ne ranki ya dad'e?" Ya fad'a yana dago fuskata da tafin hannunsa.
Na dube shi cikin wani irin yanayi ya aka yi ya san abinda yake d'auke kenan a jikin banner da logon shugunana tunda ban ta'ba daukarsa na kai shi ba kuma ban ta'ba nuna masa bidiyon abinda ya danganci harkokina ba.
Ya d'an yi murmushi yana fad'in." An gaya miki shashashan namiji kike aure Amina. Bari ki ji abinda ba ki sani ba tunda na aure ki idona akan harkokinki yake da cigaba da fad'uwa duk ina samun labari mussaman na samu lokaci Hamusu ya jagorance ni ya nuna mini shagunanki a cikin kasuwar kwari yana kuma gaya mini irin yadda nauyi da hidima suka yi yawa akan ki akwai abin mamaki ne a anan don miji ya bibiyi sha'anin matarsa. Tunda kina shakkar ki nuna mini ciki da wajenki ni na bibiya domin samun nutsuwa kuma na yi miki murna da farinciki kin zama mace mai kamar maza a cikin maza kashi dari kin take hamsin sauran sakarkarun su d'auki hamsin domin jajurcewarki akan neman halak ba kowane namiji ne zai iya abinda ki ke yi ba a yanzu kuma ina yi miki fatan alheri tare da addu'ar Allah Ya sa ki fi haka."
Tun da ya fara maganar kaina yake a sunkuye d'agowar da zan yi sai ta yi daidai da zubowar hawayen da ya taru a cikin kwarmin idona suka fara sauka saman kumatuna bakina ya dinga rawa magana nake so na yi amma gabad'aya ya gama d'aure ni da jijiyar jikina na rasa shin godiya zan yi masa ko kuma rungume shi zan yi."
Ya d'an 'bata fuska yana fad'in." Kina ba ni mamaki wasu lukutan Amina shin ni din kuwa  ina da abinda zan biya ki bisa abubuwan da na samu ta dalilinki. Kada ki manta da cewa babu wani arziki madaukaki anan duniya mai sanya farinciki da annashuwa face na haihuwa tabbas Allah ne yake bada ita bayan na yi godiya a wajensa wajibi ne kema na yi miki bisa samun sanyi idaniya da kuka ba ni. Babu buk'atar godiyarki ko zubar hawaye ina so ni ma na shiga cikin ladan da kike samu don haka don na sanya miki hannu cikin lamarinki kaina na yi wa taimako babu wanda ya san gawar fari sai Allah ko bayan babu raina ina da tabbacin yarana kaf da naki da ba naki ba ba za su wulakanta ba.''

Hannuna na sanya na sar'kafo wuyansa ina kuka sosai wanda yake fitowa daga can karkashin zuciyata. Ya d'ora hannuwansa biyu a gadon bayana yana d'an bubbugawa kafin ya dago fuskata muka dubi juna da wani irin murmushi a fuskarsa ya furta." Kukan sam bai yi miki kyau ba giwa na hango muninki." Ya sanya yatsu yana ta'be mini hanci da kumatu haka dai na dinga daurewa ina cire hannunsa yana mayarwa dole dai sai da ya sanya ni dariya ya cika mini kumatu yana fad'in ." To ko kefa kuka ko mutuwa na yi kada ki yi mini kuka domin abin sai ya zai zame mini biyu na tafi na barki wata'kila shekaru kad'an ki manta da ni wasu mazan su fara zawarcinki."
Na ce." Don Allah wace irin magana ce wannan ka daina ba ni son jinta."
Ya gyad'a kansa yana fad'in." Gaskiya ne ai Amina idan na rasu mazan zamanin nan ba za su iya d'auke ido a kan ki ba."
"Idan ka riga ni rasuwa babu yadda zan yi ba kuma zan kalubalanci Ubangiji ba domin ni ma ita nake jira amma ka sani wallahi ko shugaban kasa ne zai fito neman aurena ba zan aure shi ba na gama aure har abada zan zo na riskeka a aljanna mu cigaba da rayuwa."
Yana dariya sosai ya ce."Shugaban kasa fa Amina?' Na tare shi da saurin gaske ina cewa." Ko da sarki ne wallahi ai na gama yin rashin mijin da babu wanda ya isa ya maye mini gurbinsa to me nake nema a duniya komai ka yi mini fa."
Fuskarsa ta yawalta da wani 'kasaitancen murmushi yana ta 'kan'kance idonsa a tsakiyar nawa idon dad'in kalamaina sun sanya shi cikin wani irin shau'ki ya rasa ma abinda zai ce mini duk bakinsa da iya maganarsa na kashe shi a zaune sai murmushi.
Na cigaba da cewa." Kamar yadda ka kawo shawara hakan za a yi Plaza ta cigaba da amsa sunanta na (GIWA PLAZA) Shops din kuma AminatuAminu na amince da hakan na kuma gode bisa wannan kara da ka yi mini Ubangiji Allah Ya bar mu tare."
Ya rike hannuna na dama ya had'e yatsun waje d'aya ya d'amke sosai." Za a yi hakan in sha Allahu amma sauran shagunan ai ba ki da hurumi tunda hayarsu za ki bayar dole masu kar'ba sune suke da zabin abinda za su sayar a ciki kin gane abinda nake nufi ko?"
Na gyad'a kaina a nutse na ce.'' Na gane ni dai wurina sunansa GIWA PLAZA saboda suna ne na mussaman da babylove ya sanya mini kuma ina alfahari da sunan ya fito daga bakinsa."
Ya sa dariya har sai da duka hakoransa suka bayyana." Me yasa ba ki ta'ba nuna mini sunan na yi miki dadi ba uhumm?"
Ina murmushi na ce." Wallahi da gaske sunan dadi yake yi mini har wani tunkaho nake yi fa?"

littafin nan na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Aikuwa dadi ya ishe shi ya kwanta saman gado yana ta dariya sai kace wani shashasha ni ma ina ta ya shi yau na gama kashe masa karsashin jiki da 'yan kalaman da ba su wani sun kai sun kawo ba abin har ya ba ni tausayi  wato ita soyayya jahilar mahaukaciya ce babu talaka babu mai kudi haka zalika

babu sarakai babu attajirai duk lokacin da ta so illatarwarta sauka take yi a duk inda ta so ta yi sharafinta amma idan ba ita ba din ba ai ban ga wani dalilin da zai sanya mutumin nan yin wannan dariyar ba  wallahi.

****

Lamarin da ya kara dakusar mini  da jiki akan sha'aninsa yadda da kansa yake yi mini tallah status d'insa da kuma babban pege dinsa na facebook da Instagram bayan an gama shirya duka shagunan shidan kowanne d'ankare da kayan masu inganci da quality shaguna biyu da ya yi alkawari sai da ya shirye mini su da lates Textiles yaduka na manya da shaddodi d'ankare kowace kanta abin gwanin burgewa shagon cosmetics d'aya na supplements d'aya  d'ayan kuma na zannuwa leces atamfofi kowane nau'in da b'angaran abaya (dogayen riguna) d'ayan kuma ya zama na takalman mata da maza da kuma b'angaran huluna iri daban daban. Mussaman ya sanya masu shirya advert da muryar da lallai dole ta isar da sa'ko aka yi bidiyon na mussaman tun daga kan shagunana na kwari market har zuwa wad'annan sabbin da aka bud'e. To sanya hotonan wajan a peges din sa na sadarwa ya sanya jama'arsa yin shearing kafin ki ce me messages na 'yan uwa  sun fara cika inbox dina mussaman daga maiduguri mutum kusan shida na buk'atar samun gurbi daga cikin  dole ne a cikinsu zan duba wad'anda suka dace daga cikinsu.

Rasa abinda zance masa na yi tunda ya ce ba shi buk'atar godiya sai dai daga zarar na kalleshi sai na ji tausayinsa ya tsirga mini har ina jin taruwar hawaye a idona da kansa yake ta yi mini tallah ya cire girman kai ya cire son a sani ya kuma cire k'yashi irin na wasu mazan ya kuma nuna shi din duk arzikinsa me nema ne ya kuma tabbatar mini da cewar abinda ya yi shine kasuwanci domin kuwa shi arziki ai ba a nemansa da sau'ki. Ban yi gangancin kwatanta abinda ya yi ba a ganina yadda jama'arsa ma suke sharing ya isa gefe guda kuma daga can kano Hamusu da Usaini suma sun dage sosai da tallah ta kowace kafar sadarwa abin ya yi ta ba ni mamaki.
A daran na amsa wayar Baban Saude addu'a ce dai da fatan alheri anti Yagana Sahura Hadiza ma ta kira ni Ya Falmata kuwa kamar ma ta fi ni farinciki fadi take yi na jima da gaya miki cewa akwai haske cikin rayuwarki domin kina da nasibi gaba kad'an za ki zama abar kwantace.
Washe gari da safe kafin ya fita yake gaya mini akwai wanda suka gama magana da shi gogaggene fannin kasuwanci kuma mutum ne mai kula da amana don haka ya saya mini sabbin layikan waya shi wanda ya kira da Lawan zai zama kamar manager a wajan domin sa ido da kuma kula da yaran da za a sanya a shagunan
 sannan akwai buk'atar samar da securities saboda dukiyar da aka zuba shaguna dai tuni an kar'be su domin a yinin ranar da bidiyon ya fita duk guda shidan kyasa da sama aka kama saboda sun yi sau'ki duk kuwa da cewar an kashe kudi an kuma yi komai cikin inganci ga soler ga Ac sannan ko'ina teis kuma akan miliyan shida duk d'aya ga wurin fuskar jama'a daf da titi jama'a na hada-hada a fannin babu cunkoso mai yawa. Wallahi cikin yammacin ranar naga shigowar kud'ina miliyan talatin da shida. Ya kira ni domin ya

tabbatar  da shigowarsu ya ce kudin shagunana ne yaa katse jin na fara yin godiya abinda baya buk'ata kenan.
Sai da ya dawo yake gaya mini sun yi waya da Baban Saude har da Babanmu ma suna yi  ta yi masa godiya na ce nima duk sun kira ni sun yi mini addu'a sosai. Anti Yagana kuma tun abin nan da ya faru a lokacin da ya yi mini kyautar kamfani suke jin kunyar juna ita dashi Ya Falmata ce dai ta kira shi a waya har ta had'a shi da Dada sukai ta yi masa godiya.
Wannan shine abinda ya haddasa mummunan rikici tsakaninsa da Hauwa wanda ya kaita ga tsautsayin kunnawa gidanta wuta tunda tsabar bala'in da tashin hankali a ranar da taga abinda yake faruwa a social media da kuma status dinsa ta d'ora abinci jallop din taliya har sai ta babbake ta yi baki tana can d'aki a kwance ta manta tana ta kuka gidan ya fara canzawa da k'aurin hayaki ga mai aikinta Ladidi bata nan ta je ganin gida. Sulaimanu mai yi mata hidima gidan shi ya ankara domin masu gadi na can nesa abin bai je musu ba ya shiga gidan a gigice hayaki da kauri daga kicin tukunya ta yi jajawur gas na neman yin bindiga da ita da shi Allah ne yasa suna da nisan kwana ya yi namijin kokari sosai domin kuwa shine ya tunkari gas din ya kashe ya toshe hancinsa a gaggauce ya fita sai a lokacin ne ta fito a ki'dime ita da shi suka yi waje Ubangiji Allah Ya ta'kaita k'auri da haya'kin suka gama fita tukkuna ta koma cikin falon. To tundaga ranar suke rikici shi fad'ansa yana so ya ji dalilin da ya sanya take nema ta had'a masa gobara a gida domin dai duk b'oyenta sai da ya gane lallai akwai abinda ya faru a gidan kuma Sulaimanun bai boye masa komai ba. Ta dinga kuka tana fad'in sai ya saketa  ita gaji ya ce shi kuma haka kawai ba zai yi saki ba sai da hujja. Rikicin dai har sai da ya kai su gaban Hajja anan ne ta fad'i abinda yake sasakarta Ya gina mini  plaza ya ya zuba mini kaya sannan ya kuma bude mini  shaguna a kasuwar kwari guda uku ita kuma ya had'a ta da wani lalataccen kamfaninsa da ya tabbatar da cewa shi kansa ya tashi daga aiki don haka wallahi idan har adalci za a yi itama a yi mata plaza sannan a bude mata shaguna. To sai a lokacin ne ya san dalilin tashin hankalinta.  Ya ce yadda ya mallaka mata kamafani ba tare da ya cire na'urorin da ake aiki da su ba haka zalika don ya gina mini plaza ya sanya mini kaya a ciki ba lefi ba. Duk abinda yake yi yana sane yana kuma yin aiki da ilimi da koyarwar Annabi domin yin adalci cikin ni da ita babu wadda ta sanya shi ba mu wani abu daga cikin dukiyarsa shi ya yi ra'ayi a lokacin ya jaddadawa Hajjan cewa plaza kad'an ya yi mini a madadin kamfanin da ya bata sauran shagunan da take tunanin shi ya bud'e mini ba shi da hannu tun kafin ya aure ni nake neman kudi ita kanta Hajjan ta san da haka tunda da farko ganin yadda Hauwa ta yi bala'in shiga damuwa ta ce a samu sulhu kawai ya kar'bi kamfanin tunda ita din macace zai wahala ta iya kawo masa cigaba sai ya yi mata yadda take so. Amma jin haka sai jikinta ya kara yin sanyi tuntuni ta fahimceta zafin kishinta da ganin Ido shine zai kai ta ya baro.
Kwanansa biyu a kano suna buga artabu Hajja ta ce a sayar da kamfanin a bata kudin shi kuma ya ce bai gina shi don ya sayar ba. Adalci d'aya da zai yi mata zai cigaba da kula mata da shi domin ganin ya sake yin shura yanzu ma ba wai aiki ne ba ya yi ba, kawai dai yawaitar massarafuwar kamfanin

sabulun da suka yi yawa ya sanya kasuwarsa ta kwanta dama amma a rana akan iya fitar da kwali dubu ko fiye da haka ina lefi. Hajja ta ji dad'in hakan domin sai take ganin ba wani abun bane a ganinta ma wanda aka bawa kamfani guda ai ya fi morewa ta sallame shi ta ce ita Hauwan ta kwana biyu a wurinta domin a ganinta cikin kwanakin da za ta yi zata iya tausarta ta rarrrasheta ta ha'kura amma ina Hauwa ta wuce da tunaninta washe garin ranar da ya tashi Hajja na dyakinta da safe misalin goma da kwata tana sallar walha Hauwa ta bar gidan cikin matsanaciyar damuwa da tashin hankali bauci ta nufa zuciyarta cike da bakinciki da kuma neman hanyar da zata warware damuwarta.......✍

*GARKUWAR MATA.*

*BINTA UMAR ABBALE*

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*

*V-VIP AREWAPEN*

*07084653262*

*174*

To duk yadda ya kai da ko'karin ganin ya b'oye abinda yake damunsa sai da na hankalta cewa lallai a cikin matsanaciyar damuwa yake wadda ma take ko'karin ganin ta ta'ba wasu muhimmanan al'amuransa mussaman da ya d'auki dabi'ar shiru da nazari. Hankalina sai ya rabu biyu daya a kansa daya kuma akan harkokina da suka fara kafuwa wanda shi din ne ya zama sila kuma ma'kasudi domin dai ya taka muhimmiyar rawa wadda ta zama tushe kuma matakin nasara shaguna har mun tsayar da ranar bud'e su wadda muke sanya ran cewa a cikinta za mu yi promo ga customers dinmu na farko mun tallata daga can kano zuwa abujan da sauran jahohi bisa jagorancin mutumin da ya had'a ni dashi Lawan wanda na tabbatar da cewar shi din za'kwakuri ne tuntuni sun yi masayar lambobin waya da su Hamusu. Kuma mun gama magana da Baban Saude kan cewa zai ba ni yaransa biyu duk da acan suna sana'ar huluna da sayar da yaduka mabambamta mussaman na hijabai da ro'ko da magiya ya amince mini domin duk wad'anda suka nemi samun gurbin zama duk da cikin family dinmu suke Ya Falmata ta ce a a daya muka d'auka daga cikinsu Halifa karamin k'aninsu Banandi sai Abahuraira da kaninsa Saifullahi yaran Baban Saude daga can kano kuma gidanmu na ce idan Hamusu da Usaini za su taho sai Ashiru ya biyo su shima tunda shi Saminu suna tare da Yusi a shago daya wanda koyaushe yake sake bunkasa dalilin kokari da cigaban da suke kawo masa a zamanance. Wannan yanayin nasa gabad'aya sai ya dakusar mini da karsashin jikina hidimar dai kawai nake yi amma gabad'aya bana yin ta cikin dadi dalili ko bai gaya mini cewar akwai matsala tsakaninsa da Hauwa ba dole na gane tunda ya fi sati daya yana kwana a gidana sau d'aya da na yi masa magana ya 'bata ransa yana ba ni amsa kamar ba ya so sai ban sake ce masa komai ba na zura masa ido amma dai yau na yi niyyar takureshi akan sanin abinda yake faruwa yanzu abinda na gama fahimta a game dashi Hauwa ce matsalarsa tunda zahiri da bad'ini Allah Ya riga ya gama yi masa komai

Ilai kuwa ita din ce domin dana matsananta masa da tambaya abinda yake zuciyarsa ya furta mini Kai tsaye Amina zan saki Hauwa.
Zahiri na ji fad'uwar gaba da tashin hankali lokacin da maganar ta fito daga bakinsa ban kuma yi mamaki ba domin tsananin tunani da nazarin da yake yi akan lamarin ne shin ya aikata ko kada ya aikata tsayin shekarun zamana da shi na fahimci mutum ne mai nisan tunani kuma bai fiye yanke hukunci cikin fushi ba yakan ta jujjuya lamari yana nazari a kansa kafin ya yi hukunci ga misali nan akan matarsa Hajiya Maryam da ta rasu kafin ya amince da abinda ake magana a kanta sai da aka kai ruwa rana har ya gani da idonsa ya kuma tabbatar.
Jikina ya shika sosai na zuba masa idanuwana shima ya zuba mini nasa ido babu annuri ko kad'an a saman fuskarsa ya cigaba da cewa rabuwata da yarinyar nan shine kwanciyar hankalinmu gabad'aya domin kuwa Hauwa ba ta shirya zama ta gyara mini gidana ba har ta ba ni nutsuwa da kwanciyar hankali irin wadda nake samu a wurinki. Ni ba sakaran namiji ba ne don haka ban ga dalilin da zai sanya a ce wata mace na raba mini hankali ba. Abu biyu suke ri'ke da Hauwa a hannuna a yanzu kuma su nake dubawa shiyasa duk abubuwan da take yi nake kawar da kaina a kanta ba wai tsoron rabuwa nake da ita ba kamar yadda take nuna hakan. Ko yau na rabu da ita gobe ina iya auro wata a madadinta idan har ina da ra'ayin hakan don haka tunda kin nemi da lallai sai kin ji matsalata to wannan ce."
A kasalance na ce." Ko zan iya sanin dalili, ai dai ka san haka kawai ba a sakin mace sai da dalili, gaskiya ka yi hakuri abin kunya ne a tsakaninku dukkaninku kun girma fa."
Ya gyad'a kansa ." Dalili akan ki ne domin duk zargi da tashin hankalin da ta shiga ganin kasuwancinki tana ganin ni na kafa ki na ce mata a a ni ma cikin nema na gan ki muka yi aure kina neman ki, bata yarda ba ta kai kara wurin Hajja wai kamar ni Hauwa ke yawon kaini k'ara saboda ba ta da mutunci tana ganin na fifitaki ina kashe miki kudi ita na bata tsohon kamfani sai dai a canza mata da abinda na yi miki shin a cikinku ko akwai wadda ta sanya ni d'aukar dukiyata na baku, alheri ne kawaii na yi muku ganin tare duka aka nemi dukiyar daku tana ganin abinda na yi miki ya fi wanda na yi mata akan hakan kuwa lallai ranta zai b'aci don ban ga dalilin da zai sanya ta tsananta k'yashi a kan ki ba, kema Allah ne ya yi miki daidai gwargwado kuma kin nema ni hannu kawai nasa miki kuma sai daga karshe ko ba haka ba ne?"
Na gyad'a kaina ina fad'in." Hakane amma akan hakan ka ke cewa za ka saketa ai ba hujja ba ce wannan kuma abinda ta nema ka fi karfinsa don ta tsananta kishi da k'yashi a kaina babu lefi ko ka manta kishi ne a tsakaninmu kowa fa da irin zuciyarsa, wallahi ban ji komai ba amma don girman Allah in dai zan baka shawara ka d'auka to ka yi mata yadda take so tunda kana da iko ka daidaita tsakaninmu itama ka bude mata plazar sai ka kar'bi kamfanin ka kawai tunda dama wahalarsa yawa gareta."
Ya girgiza kansa." Idan na yi mata plaza sauran shops din na kwari market kuma wa zai yi mata? tana cewa ai duk ni na yi miki"
Yar dariya na yi kad'an na ce sai ka yi mata menene a ciki ai Allah Ya hore maka?"

Ya girgiza kansa a nutse ya furta." Babu wanda zai karya mini rantsuwa Giwa ai na ce ta bar shi a hannuna zan a cigaba da aiki da shi a madadinta kuma abinda take han'koro za ta samu rashin yarda ne kawai da ci da zucci. Ba zan yi wata plaza ba yanzu wannan shine karshen magana."
"To kasan halinta da rashin yarda da kuma taurin kai kenan idan kai da kake matsayin jagora baka yi yun'kurin ganin ka nemo mafita ba lamarin zai lalace ai."
"Ai na nemi mafita tuntuni aiwatarwa zan yi kawai ko kin ga na yi miki kama da namijin da mace za ta juya ne Amina. Wasu lukatan Kawai ina biye muku ne domin ba na son hayaniya wa za ta gayawa taurin kai ne ni da ita shege ka fasa."
D'akin ya d'auki shiru bayan ajiye maganarsa na sauke numfashi Ina dubansa na ce." Yanzu kasan yadda za a yi tunda abin ya zo da haka me yasa ba za ka kara mata kudi akan kamfanin ba."
Harara ya wurgo mini kafin ya ja tsaki yana fadin. "Ba zan k'ara mata ko kwabo ba wallahi."
Rantsuwar da ya yi a karon farko sai jikina ya mutu ba wai bashi dashi ba ne bayarwa ne kawai ba zai yi ba Amma ni ina ganin idan har ya k'ara mata kudi akan kamfanin da take ganin darajarsa ba ta kai plazata ba zuciyarta zata yi sanyi ga shi kuma ya rantse da gaggawa.
Na ce." To ni zan k'ara mata amma a madadinka."
Ya dinga shillo mini harara kafin ya yun'kura ya tashi bai ce komai ba ya shige toilet yana tsaki. Ni kuma a ganina ai ba abin jin haushi ba ne don zan bata kud'i ba ni son ya saketa ko kad'an wallahi domin abin ba zai yi mata kyau ba daraja dai da alfarmar tana a hannunsa ta yi hakuri ta barwa Allah ikonsa kamar yadda ya fadi yanzu Ubangiji ne ya yi mini wallahi ban ta'ba tunanin zan kai matakin da nake a yanzu ba.
Kwanaki biyu muna ta abu daya gabad'aya ma ya'ki ya saurare ni da shawarar da na kawo sai hanya hanya yake yi yana ta shirye-shiryen tafiya Legos abinsa ni kima ina ta damuwa ga ciwo ciwon da na fara cin karo da su na kasala da zazza'bi taruwar yawu a baki da yawan bacci ciki ne da ni na tabbatar domin ban ga al'adata ba rashin sukuni da abubuwan da suka kutso ya sanya bai lura da canje-canjen da na sake samu ba.
Cikin wannan yanayin muka bude shagunanmu da bisimillah abin sai godiya da sake godiya wurin Ubangiji mun samu alheri kwarai da gaske domin yanayin yadda aka s'aukaka farashi a karon farko ya sake janyo mana suna a duniya da costumer's mabambamta. Daga cikin manema labarai ('yan jarida) har da ni Binta Umar Abbale na tafi da biro da takardata domin d'auko rahoto na samu abin rubutu a kai
Na shiga cikin mutane ina ta ra'be-ra'be duk na ki'dime hankalina ya kasu kashi -kashi shin rahoton zan d'auko ko kuwa kallon zan yi kaya na alfarma kamar za su bud'e ido jama'a kuwa ga su nan hamsha'kai suna ta parking din motocinsu
Allah sarki ashe ta hango ni a labe ina le'ken shagon supplements dinta da ya tumbatsa da ya kaya ni shine ya yi bala'in d'auke mini hankali na saki baki galala ina ta hango manyan supplements din da suke tumbatsar da

mace da tayar mata da komad'ar jiki cikin zuciyata ina ta fad'in dama ina da kud'i zahiri da na sayi wanda zai dawo ni shamshakiyya kalar 'yan gayu irinta duk da yake supplements din kala kala ne amma dai ga dukkanin alamu duk abinda yake cikin wannan shamsh'akin shagon nata sahihi ne babu cutarwa. 08089965176 domin neman karin bayani Aikuwa ganina sai ta yafitoni da hannu da wannan fara'arta tata ta ce da ni na za'bi abinda nake so. Na dinga washe bakina don saura kad'an na daka tsallen murna na ajiye 'yar zabirata a can wani waje inda wani mutum yake zaune da Loptop a gabansa amma ban iya ajiye biro da doguwar pepper din da take hannuna ba.
kai tsaye shagon na kutsa ina zagaye shi bakina ya ki rufuwa.
Wani kwando nai zurfi na ciko da supplements ina ayyanawa a raina Allah Ya sa kada ta ce sun yi yawa na mayar ni kaina nasan na so zuciya amma cikin ikon Allah ta kar'ba ta dudduba tana murmushi ta ce a zuba mini a leda.
Na yi ta godiya na kar'ba ina duba jikin ledar wadda ta kasance ta mussaman mai d'auke da logo da bayanai bambamta a jiki.
Daf da zan fita kawai na hangi wasu mata masu kumari sun k'oshi 'kwarai daka gani sun ci sun tayar da kai
suna ko'karin kutsa kansu shangon zannuwa. Kowacce rataye da jaka sai na bi bayansu ina ji suna fad'in dole kam ai Amina ta mu ce dole mu yi patronizing d'inta duk dai ta kafu ta tsaya da k'afafunta amma yadda ta yi kwasha-kwasa da kayanta irin haka ba kowane d'an kasuwa ne zai iya yin abinda ta yi ba. La'bewa na yi inda ba za su gan ni ba don da kunya ace ta sake ganina tunda ta sallame ni  bayan sun shiga sai na le'ka kaina abinda ya ba ni mamaki bai wuce ganin yadda suke gaisawa cikin raha da wasa da dariya ba ashe k'awayenta ne Nahajarama Maryam Saminu Sulaiman Maman Fu'ad da Mama Hauwa zaria na yi zuru ina ta lek'ensu suna ta hira ta sanya an basu wurin zama har da lemo bayan sun gama hutawa suka tashi suka fara dudduba shops din suna sanya albarka da fatan alheri. Can na hangi wasu iyayena suma sun shigo plazar cikin annashuwa ban yi mamaki ba domin dai duk cikinsu babu mutuniyar banza mata ne nagartattun da suka mayar da d'an wani nasu Hajia Usainakaita Mommy fossima Nijar hajia Halima wada kura  hajia karimatu Haladu Nasiru da hajia Halima Dalha shehu. Na kuwa ji dadin ganin yadda ta karrama mini iyaye suma kuma sun yi mata halin karamci  da dattako turaman atamfofi suka saya masu yawan gaske wanda nake da tabbacin cewa ba d'aurawa za su yi a jikinsu ba rabar da su za su yi ga iyayan marayu.
Ina nan tsaye da ledar kayana na hangi k'awayen nan nata sun fito kowacce da ledoji a hannunta niki-niki ita kuma ta biyo bayansu da raha da barkwanci na yi saurin b'oye kaina ta raka su har bakin motarsu suna yin sallama hannuwansu ri'ke da juna kamar kada su rabu.
Na sake gyara biro da takardar dake hannu ina kallonsu da wani irin murmushi wanda ni kaina na kasa gane ko na menene lallai Amina ta cancanci k'auna da soyayya domin kyawawan halayenta..

****

To cikin sa'a aka kammala bikin bude shops wanda aka d'auki tsayin sati guda ana kai kawo da hidima da jama'a cikin k'warewa da jajurcewa ta kowane fanni anyi katari kuwa domin kuwa an cimma nasara akan abinda ake nema.

Duk nisha'din da cigaban da na samu ban samu nutsuwa yadda ya kamata ba domin kuwa har yanzu maigidan ba a nutse yake ba yana dai ta yin al'amuransa ne a matsayinsa na namiji mai juria amma ni da nake tare da shi na kuma san halinsa na san a cikin damuwa yake kawai yana danneta ne. Kuma na gaya masa a wannan tsukin da shi kansa ya kasa control din matsalarsa yana da kyau ya tsananta da addu'a domin neman zabin Allah amma zahiri shirinsa da yanayin yadda yake kasancewa cikin damuwa ya fara damuna ina ganin dole na sanya hannuna a wannan rikicin duk kuwa da alwashin da na ci a baya a kan fita daga sabgarta don ganin ya fita daga cikin damuwar da yake cikinta a yanzu.

Yadda Allah Ya yi mini babu wayo kuma babu dabarata dalili kuwa in banda ni da yaran shops dina a yanzu babu wanda yasan adadin alherin da na samu a cikin kwanakin nan kacal shi kansa bai sani ba kuma ina so na gaya masa na samu riba da yawa a cikinta zan cire wani abu na bawa Hauwa tunda shi ya riga ya rantse ba kuma na so na karya masa rantaywarsa.

Ranar dana gaya masa zan cire 10m shima ya cire 10m mu had'a mata 20m kawai ya ji ne amma uffan bai ce mini ba har garin Allah Ya waye bai sake tayar da maganar ba ni ma ban tasheta ba sai bayan kwana biyu na sake yi masa magana. Aikuwa ya fara fad'a sosai kamar dama kiris yake jira yana fad'in kamfani ya yi niyyar bata tunda ta ce bata so kanta ta yi wa kwabonsa ba zai k'ara mata ba. Tunda nayi niyya na bata kud'ina ne amma shi ba a isa ba.
Sai na kyale shi kawai bayan kwana biyu na kira Hajja a waya muka gaisa sosai na sha addu'a da fatan alheri domin Hamusu ya kai mata turaman atamfofin da na ce a dinka mata anan ta dinga godiya da addu'a har sai da na ji hawaye ya ciko idona ba zan yi maraicin uwa ba tunda Hajja tana raye bata yi mini k'yashi da ba'kinciki irin na wasu iyayen mijin ko wannan alherin ya isa ni ma na ture komai. Duk da bani da hurumi akan lamarin amma Allah ya ga nufi ne sam ba ni yi wa Hauwa sha'awar abinda take yi wa kanta hasashe yadda ya d'auki wannan zafin wallahi kiris ya rage a yi ta kare. Duk shawarar da na yanke na gaya mata domin kuwa ko anti Yagana ban gayawa ba duk da nasan bata da ganin k'yashi amma za ta iya hana ni tace babu ruwana.
Wannan maganar tawa ta yi wa Hajja bazata ainun ta rasa abinda zata ce sai da na ji shurun ta yi yawa tukkuna na sake magana sannan na ji sautinta tana ta godiya tana sanya albarka tana fad'in tunda shi ya rantse ba zai k'ara mata komai ba to itama ta sanya 5m sai a had'a mata 15m na ce hakan ya yi amma da sunan duka ita ta bata kada sunana ya fito ciki. Ta ce hakan ba hujja ba ce dole a gaya mata jin ta fad'i haka sai na gane cewar ba ta fahimci

azancina ba. Na jima kuwa ina yi mata bayani idan har Hauwa ta tabbatar da cewa ni ce ma na bata kudi ba shi ba ko ita Hajjan  to babu shakka wutar ba zata mutu ba ruruwa ma zata sake yi tunda duk rikicin a kaina ne. Tsayin lokacin da na d'auka ina yi mata bayani ya sanya ta gane hujjata sai ta amince da hakan tana ta sanya mini albarka da addu'a akan Allah Ya ninka mini abinda na bayar ya kuma albarkaci kasuwancina.........✍

[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*174*
To duk yadda ya kai da ko'karin ganin ya b'oye abinda yake damunsa sai da na hankalta cewa lallai a cikin matsanaciyar damuwa yake wadda ma take ko'karin ganin ta ta'ba wasu muhimmanan al'amuransa mussaman da ya d'auki dabi'ar shiru da nazari. Hankalina sai ya rabu biyu daya a kansa daya kuma akan harkokina da suka fara kafuwa wanda shi din ne ya zama sila kuma ma'kasudi domin dai ya taka muhimmiyar rawa wadda ta zama tushe kuma matakin nasara shaguna har mun tsayar da ranar bud'e su wadda muke sanya ran cewa a cikinta za mu yi promo ga customers dinmu na farko mun tallata daga can kano zuwa abujan da sauran jahohi bisa jagorancin mutumin da ya had'a ni dashi Lawan wanda na tabbatar da cewar shi din za'kwakuri ne tuntuni sun yi masayar lambobin waya da su Hamusu. Kuma mun gama magana da Baban Saude kan cewa zai ba ni yaransa biyu duk da acan suna sana'ar huluna da sayar da yaduka mabambamta mussaman na hijabai da ro'ko da magiya ya amince mini domin duk wad'anda suka nemi samun  gurbin zama duk da cikin family dinmu suke Ya Falmata ta ce a a daya muka d'auka daga cikinsu Halifa karamin k'aninsu Banandi sai Abahuraira da kaninsa Saifullahi yaran Baban Saude daga can kano kuma gidanmu na ce idan Hamusu da Usaini za su taho sai Ashiru ya biyo su shima tunda shi Saminu suna tare da Yusi a shago daya wanda koyaushe yake sake bunkasa dalilin kokari da cigaban da suke kawo masa a zamanance. Wannan yanayin nasa gabad'aya sai ya dakusar mini da karsashin jikina hidimar dai kawai nake yi amma gabad'aya bana yin ta cikin dadi dalili ko bai gaya mini cewar akwai matsala tsakaninsa da Hauwa ba dole na gane tunda ya fi sati daya yana kwana a gidana sau d'aya da na yi masa magana ya 'bata ransa yana ba ni amsa kamar ba ya so sai ban sake ce masa komai ba na zura masa ido amma dai yau na yi niyyar takureshi  akan sanin abinda yake faruwa yanzu abinda na gama fahimta a game dashi Hauwa ce matsalarsa tunda zahiri da bad'ini Allah Ya riga ya gama yi masa komai
Ilai kuwa ita din ce domin dana matsananta masa da tambaya abinda yake zuciyarsa ya furta mini Kai tsaye Amina zan saki Hauwa.
Zahiri na ji fad'uwar gaba da tashin hankali lokacin da maganar ta fito daga bakinsa ban kuma yi mamaki ba domin tsananin tunani da nazarin da yake yi

akan lamarin ne shin ya aikata ko kada ya aikata tsayin shekarun zamana da shi na fahimci mutum ne mai nisan tunani kuma bai fiye yanke hukunci cikin fushi ba yakan ta jujjuya lamari yana nazari a kansa kafin ya yi hukunci ga misali nan akan matarsa Hajiya Maryam da ta rasu kafin ya amince da abinda ake magana a kanta sai da aka kai ruwa rana har ya gani da idonsa ya kuma tabbatar.
Jikina ya shika sosai na zuba masa idanuwana shima ya zuba mini nasa ido babu annuri ko kad'an a saman fuskarsa ya cigaba da cewa rabuwata da yarinyar nan shine kwanciyar hankalinmu gabad'aya domin kuwa Hauwa ba ta shirya zama ta gyara mini gidana ba har ta ba ni nutsuwa da kwanciyar hankali irin wadda nake samu a wurinki. Ni ba sakaran namiji ba ne don haka ban ga dalilin da zai sanya a ce wata mace na raba mini hankali ba. Abu biyu suke ri'ke da Hauwa a hannuna a yanzu kuma su nake dubawa shiyasa duk abubuwan da take yi nake kawar da kaina a kanta ba wai tsoron rabuwa nake da ita ba kamar yadda take nuna hakan. Ko yau na rabu da ita gobe ina iya auro wata a madadinta idan har ina da ra'ayin hakan don haka tunda kin nemi da lallai sai kin ji matsalata to wannan ce."
A kasalance na ce." Ko zan iya sanin dalili, ai dai ka san haka kawai ba a sakin mace sai da dalili, gaskiya ka yi hakuri abin kunya ne a tsakaninku dukkaninku kun girma fa."
Ya gyad'a kansa ." Dalili akan ki ne domin duk zargi da tashin hankalin da ta shiga ganin kasuwancinki tana ganin ni na kafa ki na ce mata a a ni ma cikin nema na gan ki muka yi aure kina neman ki, bata yarda ba ta  kai kara wurin Hajja wai kamar ni Hauwa ke yawon kaini k'ara saboda ba ta da mutunci tana ganin na fifitaki ina kashe miki kudi ita na bata tsohon kamfani sai dai a canza mata da abinda na yi miki shin a cikinku ko akwai wadda ta sanya ni d'aukar dukiyata na baku, alheri ne kawaii na yi muku ganin tare duka aka nemi dukiyar daku tana ganin abinda na yi miki ya fi wanda na yi mata akan hakan kuwa lallai ranta zai b'aci don ban ga dalilin da zai sanya ta tsananta k'yashi a kan ki ba, kema Allah ne ya yi miki daidai gwargwado kuma kin nema ni hannu kawai nasa miki kuma sai daga karshe ko ba haka ba ne?"
Na gyad'a kaina ina fad'in." Hakane amma akan hakan ka ke cewa za ka saketa ai ba hujja ba ce wannan kuma abinda ta nema ka fi karfinsa don ta tsananta kishi da k'yashi a kaina babu lefi ko ka manta kishi ne a tsakaninmu kowa fa da irin zuciyarsa, wallahi ban ji komai ba amma don girman Allah in dai zan baka shawara ka d'auka to ka yi mata yadda take so tunda kana da iko ka daidaita tsakaninmu itama ka bude mata plazar sai ka kar'bi kamfanin ka kawai tunda dama wahalarsa yawa gareta."
Ya girgiza kansa." Idan na yi mata plaza sauran shops din na kwari market kuma wa zai yi mata? tana cewa ai duk ni na yi miki"
Yar dariya na yi kad'an na ce sai ka yi mata menene a ciki ai Allah Ya hore maka?"
Ya girgiza kansa a nutse ya furta." Babu wanda zai karya mini rantsuwa Giwa ai na ce ta bar shi a hannuna zan a cigaba da aiki da shi a madadinta kuma abinda take han'koro za ta samu rashin yarda ne kawai da ci da zucci. Ba zan yi wata plaza ba yanzu wannan shine karshen magana."

"To kasan halinta da rashin yarda da kuma taurin kai kenan idan kai da kake matsayin jagora baka yi yun'kurin ganin ka nemo mafita ba lamarin zai lalace ai."
"Ai na nemi mafita tuntuni aiwatarwa zan yi kawai ko kin ga na yi miki kama da namijin da mace za ta juya ne Amina. Wasu lukatan Kawai ina biye muku ne domin ba na son hayaniya wa za ta gayawa taurin kai ne ni da ita shege ka fasa."
D'akin ya d'auki shiru bayan ajiye maganarsa na sauke numfashi Ina dubansa na ce." Yanzu kasan yadda za a yi tunda abin ya zo da haka me yasa ba za ka kara mata kudi akan kamfanin ba."
Harara ya wurgo mini kafin ya ja tsaki yana fadin. "Ba zan k'ara mata ko kwabo ba wallahi."
Rantsuwar da ya yi a karon farko sai jikina ya mutu ba wai bashi dashi ba ne bayarwa ne kawai ba zai yi ba Amma ni ina ganin idan har ya k'ara mata kudi akan kamfanin da take ganin darajarsa ba ta kai plazata ba zuciyarta zata yi sanyi ga shi kuma ya rantse da gaggawa.
Na ce." To ni zan k'ara mata amma a madadinka."
Ya dinga shillo mini harara kafin ya yun'kura ya tashi bai ce komai ba ya shige toilet yana tsaki. Ni kuma a ganina ai ba abin jin haushi ba ne don zan bata kud'i ba ni son ya saketa ko kad'an wallahi domin abin ba zai yi mata kyau ba daraja dai da alfarmar tana a hannunsa ta yi hakuri ta barwa Allah ikonsa kamar yadda ya fadi yanzu Ubangiji ne ya yi mini wallahi ban ta'ba tunanin zan kai matakin da nake a yanzu ba.
Kwanaki biyu muna ta abu daya gabad'aya ma ya'ki ya saurare ni da shawarar da na kawo sai hanya hanya yake yi yana ta shirye-shiryen tafiya Legos abinsa ni kima ina ta damuwa ga ciwo ciwon da na fara cin karo da su na kasala da zazza'bi taruwar yawu a baki da yawan bacci ciki ne da ni na tabbatar domin ban ga al'adata ba rashin sukuni da abubuwan da suka kutso ya sanya bai lura da canje-canjen da na sake samu ba.
Cikin wannan yanayin muka bude shagunanmu da bisimillah abin sai godiya da sake godiya wurin Ubangiji mun samu alheri kwarai da gaske domin yanayin yadda aka s'aukaka farashi a karon farko ya sake janyo mana suna a duniya da costumer's mabambamta. Daga cikin manema labarai ('yan jarida) har da ni Binta Umar Abbale na tafi da biro da takardata domin d'auko rahoto na samu abin rubutu a kai
Na shiga cikin mutane ina ta ra'be-ra'be duk na ki'dime hankalina ya kasu kashi -kashi shin rahoton zan d'auko ko kuwa kallon zan yi kaya na alfarma kamar za su bud'e ido jama'a kuwa ga su nan hamsha'kai suna ta parking din motocinsu
Allah sarki ashe ta hango ni a labe ina le'ken shagon supplements dinta da ya tumbatsa da ya kaya ni shine ya yi bala'in d'auke mini hankali na saki baki galala ina ta hango manyan supplements din da suke tumbatsar da mace da tayar mata da komad'ar jiki cikin zuciyata ina ta fad'in dama ina da kud'i zahiri da na sayi wanda zai dawo ni shamshakiyya kalar 'yan gayu irinta duk da yake supplements din kala kala ne amma dai ga dukkanin alamu duk abinda yake cikin wannan shamsh'akin shagon nata sahihi ne babu cutarwa.

08089965176 domin neman karin bayani Aikuwa ganina sai ta yafitoni da hannu da wannan fara'arta tata ta ce da ni na za'bi abinda nake so. Na dinga washe bakina don saura kad'an na daka tsallen murna na ajiye 'yar zabirata a can wani waje inda wani mutum yake zaune da Loptop a gabansa amma ban iya ajiye biro da doguwar pepper din da take hannuna ba.
kai tsaye shagon na kutsa ina zagaye shi bakina ya ki rufuwa.
Wani kwando nai zurfi na ciko da supplements ina ayyanawa a raina Allah Ya sa kada ta ce sun yi yawa na mayar ni kaina nasan na so zuciya amma cikin ikon Allah ta kar'ba ta dudduba tana murmushi ta ce a zuba mini a leda.
Na yi ta godiya na kar'ba ina duba jikin ledar wadda ta kasance ta mussaman mai d'auke da logo da bayanai bambamta a jiki.
Daf da zan fita kawai na hangi wasu mata masu kumari sun k'oshi 'kwarai daka gani sun ci sun tayar da kai
suna ko'karin kutsa kansu shangon zannuwa. Kowacce rataye da jaka sai na bi bayansu ina ji suna fad'in dole kam ai Amina ta mu ce dole mu yi patronizing d'inta duk dai ta kafu ta tsaya da k'afafunta amma yadda ta yi kwasha-kwasa da kayanta irin haka ba kowane d'an kasuwa ne zai iya yin abinda ta yi ba. La'bewa na yi inda ba za su gan ni ba don da kunya ace ta sake ganina tunda ta sallame ni  bayan sun shiga sai na le'ka kaina abinda ya ba ni mamaki bai wuce ganin yadda suke gaisawa cikin raha da wasa da dariya ba ashe k'awayenta ne Nahajarama Maryam Saminu Sulaiman Maman Fu'ad da Mama Hauwa zaria na yi zuru ina ta lek'ensu suna ta hira ta sanya an basu wurin zama har da lemo bayan sun gama hutawa suka tashi suka fara dudduba shops din suna sanya albarka da fatan alheri. Can na hangi wasu iyayena suma sun shigo plazar cikin annashuwa ban yi mamaki ba domin dai duk cikinsu babu mutuniyar banza mata ne nagartattun da suka mayar da d'an wani nasu Hajia Usainakaita Mommy fossima Nijar hajia Halima wada kura  hajia karimatu Haladu Nasiru da hajia Halima Dalha shehu. Na kuwa ji dadin ganin yadda ta karrama mini iyaye suma kuma sun yi mata halin karamci  da dattako turaman atamfofi suka saya masu yawan gaske wanda nake da tabbacin cewa ba d'aurawa za su yi a jikinsu ba rabar da su za su yi ga iyayan marayu.
Ina nan tsaye da ledar kayana na hangi k'awayen nan nata sun fito kowacce da ledoji a hannunta niki-niki ita kuma ta biyo bayansu da raha da barkwanci na yi saurin b'oye kaina ta raka su har bakin motarsu suna yin sallama hannuwansu ri'ke da juna kamar kada su rabu.
Na sake gyara biro da takardar dake hannu ina kallonsu da wani irin murmushi wanda ni kaina na kasa gane ko na menene lallai Amina ta cancanci k'auna da soyayya domin kyawawan halayenta..

****

To cikin sa'a aka kammala bikin bude shops wanda aka  d'auki  tsayin sati guda  ana kai kawo da hidima da jama'a cikin k'warewa da jajurcewa ta kowane fanni anyi katari kuwa domin kuwa  an cimma nasara akan abinda ake nema.

Duk nisha'din da cigaban da na samu ban samu nutsuwa yadda ya kamata ba domin kuwa har yanzu maigidan ba a nutse yake ba yana dai ta yin al'amuransa ne a matsayinsa na namiji mai juria amma  ni da nake tare da shi na kuma san halinsa na san a cikin damuwa yake kawai yana danneta ne. Kuma na gaya masa a wannan tsukin da shi kansa ya kasa control din matsalarsa yana da kyau ya tsananta da addu'a domin neman zabin Allah amma zahiri shirinsa da yanayin yadda yake kasancewa cikin damuwa ya fara damuna ina ganin dole na sanya hannuna a wannan rikicin duk kuwa da alwashin da na ci a baya a kan fita daga sabgarta don ganin ya fita daga cikin damuwar da yake cikinta a yanzu.

Yadda Allah Ya yi mini babu wayo kuma babu dabarata dalili kuwa in banda ni da yaran shops dina  a yanzu babu wanda yasan adadin alherin da na samu a cikin kwanakin nan kacal shi kansa bai sani ba kuma ina so na gaya masa na samu riba da yawa a cikinta zan cire wani abu na bawa Hauwa tunda shi ya riga ya rantse ba kuma na so na karya masa rantaywarsa.

Ranar dana gaya masa zan cire 10m shima ya cire 10m mu had'a mata 20m kawai ya ji ne amma uffan bai ce mini ba har garin Allah Ya waye bai sake tayar da maganar ba ni ma ban tasheta ba sai bayan kwana biyu na sake yi masa magana. Aikuwa ya fara fad'a sosai kamar dama kiris yake jira yana fad'in kamfani ya yi niyyar bata tunda ta ce bata so kanta ta yi wa kwabonsa ba zai k'ara mata ba. Tunda nayi niyya na bata kud'ina ne amma shi ba a isa ba.
Sai na kyale shi kawai bayan kwana biyu na kira Hajja a waya muka gaisa sosai na sha addu'a da fatan alheri domin Hamusu ya kai mata turaman atamfofin da na ce a dinka mata anan  ta dinga godiya da addu'a har sai da na ji hawaye ya ciko idona ba zan yi maraicin uwa ba tunda Hajja tana raye bata yi mini k'yashi da ba'kinciki irin na wasu iyayen mijin ko wannan alherin ya isa ni ma na ture komai. Duk da bani da hurumi akan lamarin amma Allah ya ga nufi ne sam ba ni yi wa Hauwa sha'awar abinda take yi wa kanta hasashe yadda ya d'auki wannan zafin wallahi kiris ya rage a yi ta kare. Duk shawarar da na yanke na gaya mata domin kuwa ko anti Yagana ban gayawa ba duk da nasan bata da ganin k'yashi amma za ta iya hana ni tace babu ruwana.
Wannan maganar tawa ta yi wa Hajja bazata ainun ta rasa abinda zata ce sai da na ji shurun ta yi yawa tukkuna na sake magana sannan na ji sautinta tana ta godiya tana sanya albarka tana fad'in tunda shi ya rantse ba zai k'ara mata komai ba to itama ta sanya 5m sai a had'a mata 15m na ce hakan ya yi amma da sunan duka ita ta bata kada sunana ya fito ciki. Ta ce hakan ba hujja ba ce dole a gaya mata jin ta fad'i haka sai na gane cewar ba ta fahimci azancina ba. Na jima kuwa ina yi mata bayani idan har Hauwa ta tabbatar da cewa ni ce ma na bata kudi ba shi ba ko ita Hajjan  to babu shakka wutar ba zata mutu ba ruruwa ma zata sake yi tunda duk rikicin a kaina ne. Tsayin lokacin da na d'auka ina yi mata bayani ya sanya ta gane hujjata sai ta

amince da hakan tana ta sanya mini albarka da addu'a akan Allah Ya ninka mini abinda na bayar ya kuma albarkaci kasuwancina.........✍
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK.*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*175*
Bayan kwanaki biyu da kanta Hajjan ta kira ni a waya tana yi mini bayanin cewa an daidaita komai yanzu haka ma suna tare da Hauwa a gidanta da kuma mahaifiyarta kamar yadda muka yi da ita bata nuna musu da sanya hannuna ba kawai dai ta kira su ne akan su zo a tattauna domin samun maslaha kudi kuma ta kar'ba a madadin shi ya bayar domin itama ba ta nuna musu da sanya hannunta a ciki ba. Hakan ya kwantar da tarzomar da take yun'kurin tashi da uwar da 'yarta ta duka bakinsu d'aya dama tuntuni Inna Uwani ta daina b'oye -boye yanzu fili take fitowa ta nuna tana bayan d'iyarta tunda ta sha fadi cewa itace gorar gida ko ma baya. Ita Hauwa tun kafin su amsa kiran Hajjan yan-uwanta da k'awaye abokanan arziki suna ta yi mata fad'a da nuna mata daburun zama da miji da kishiya anti Zeey wato Zainab Khabir Ishak tana d'aya daga cikin wad'anda suka dinga nusashshe da ita cewar wannan abinda take yi bashi ne zai ri'ke ta a gidan aure ba domin yanzu kai ya waye an daina irin wannan kishin irin na jahilan mata da yake macace mai tsage gaskiya duk d'acinta ba ta yi shakkarta ba ta gaya mata kuskure da lefinta ta gaya mata cewa lallai ne fa sai ta gyara halinta zata cigaba da jin dad'in zama da mijinta tunda har ya iya k'ara mata miliyan goma sha biyar bayan kamfanin da ya mallaka mata to lallai  hakan ya nuna yana son cigaba da zama da ita. Ita kuwa Mum Sajeeda takaicin abinda Hauwan take yi gabad'aya ya 'kumeta ta rasa ma abinda za ta ce saboda yadda take jin haushinta tana fad'in kamar wadda ba ta yi boko ba tana aikata ayyuka irin na gidadawa mata k'awar Sadiya ta wurin aikinsu nan ma ta ji labarin abinda yake faruwa har gida ta je ta samu Hauwan ta yi mata wankin babban bargo acan wajan aiki suna kiranta da anti Hally  macace mara son wargi sannan tana da zafi-zafi mafiakasarin masu sunan suna da fad'a da kuma fad'in gaskiya komai d'acinta. Haka dai suka yi mata rubdugu a can bauchin Maman Ummul-kairi ta zauna da ita a tsanake ita cikin nutsuwa ta dinga jan hankalinta tana sake jadadda mata cewar ita kishiya ba a cin ta da ya'ki irin na bayyane tunda har ta fahimci abokiyar zamanta ta fita soyuwa a zuciyar mijinsu sai ta nemi hanyar ganin ta samu zaman lafiya da ita Asmau Muhammad jabbi ta sanya bakinta tana cewa kuma ta ji an ce kishiyartata bata da mugunta sannan macace mai karamci da halin girma mussaman idan an duba da irin abubuwan da ta gudanar a cikin kwanakin da suka gabata wurin sassauto da farashin kayanta. Ita kuwa Eama kallon sakarai take yi mata domin tun tana bata haushi yanzu dariya take bata tana kiranta da sokuwar mace
 Aishatu waziri kuwa fadi take yi ki gurgu'de auren ki dawo ki zauna a gida wallahi akwai wadda na yi masa sha'awarta kuma a cikin mu take duk yadda

zan yi sai na yi kokarin ganin ya nemi auranta tunda ke baki da wayo  kin gama bayyanawa miji da kishiya munanan halayenki.

***

To ni dai Hajja bata gaya mini ranar da za ta dawo ba amma hankalina ya kwanta sosai jin cewar komai ya daidaita har ta kar'bi kudi to na tabbatar da cewar kuwa ba zata kara yin wasu kwanakin masu tsayi ba za ta dawo dakinta

Yanayin yadda yake tafiyar da al'amarunsa ban tsammaci ya san abinda yake faruwa ba gaskiya domin kuwa da ya sani tabbas sai ya yi mini maganar amma gashi yau har kwana biyu da yin waya da Hajja ban ji ya ce komai ba.

Sai da daddare tukkuna bayan ya gama cin abinci ya dube ni a nutse yana fad'in."  Kin dawo da Hauwa ashe."

shiru na yi ban ce komai ba sai aunar maganar da ya yi nake yi.

Ya tsira mini ido kafin ya cigaba da cewa." Tunda kin dawo da ita sai ki gaya mata zamanki take yi babu yawuna ba kuma ruwana da ita."

Jikina ya yi sanyi ganin ta hanyar da ya 'bullo kuma hakan bai yi masa ba kenan haushi ya ji.

Na daure na furta." Ba ni da na dawo da ita ba Hajja ce."

Ya d'an harare ni yana fad'in." Duk abinda ki ka aikata mahaifiyata ta sanar da ni. Ita dai kin yi mata gwaninta kuma ta yi miki addu'a amma ni sam ba ki burge ni ba."

Na yi shiru ina kallonsa kafin ya cigaba da cewa." Tunda kudin cizonki suke yi mai zai sanya ba ki sayi fili kin yi k'aramin massalaci ba hadiya ga mahaifiyarki ko ki yi rijiyoyi na ruwa ko kuwa ki kai gidan marayu sam baki burge ni ba wallahi idan ma don ni ki ka yi bai ban sha'awa ba.

Shiru na yi na kasa tanka masa saboda jin haushin gwaliyar da yake yi mini.

Ganin ban ce komai ba sai ya cigaba da sakin maganganu na gaji da sauri na daga masa hannu ina fadin." Ni don Allah na yi ai ba don na burgeka ba tunda Hajja ta yi farinciki kuma hakan ya yi mata daidai alhamdulillahi maganar ta mutu haka don Allah."

Ya tashi zaune sosai yana kallona kafin ya ce." Magana ba zata mutu ba tunda ba ni na ce Hauwa ta dawo ba na gama yanke hukunci a kanta."

Na ce." To tunda ka gama yanke hukunci a kanta sai kawai ka aiwatar ni ina ruwana idan ka saketa ka tabbatar da cewar zaka auro wadda zata kula da yaranta ni ma nawa kadai zan ri'ke shikkenan karshen magana. "

Na yun'kuri na tashi na bashi waje.

Washe gari har d'akina ya biyo ni ina toilet ina ta kalato amai irin na sassafe majina ce kawai ke fita wani abu ya tsaye mini a wuya yana kaikayi.

Ya leko toilet din ganin halin da nake ciki sai jikinsa ya yi sanyi ya rike mini hannu har na gama na wanke bakina muka fito zuciya sai hantsilawa take yi.

Muka zauna ina ta sauke numfashi shi kuma ya tsira mini ido sosai a hankali ya furta" cikin ne ko?"

Juyar da kaina na yi ban bashi amsa ba saboda har yanzu haushin abinda ya yi mini jiya nake yi

Ya lalubi wayarsa dake cikin aljihu jikinsa na dan rawa still hannunsa na ri'ke da nawa  lambar wayar Dr Sailuba yake nema.
Na kar'bi wayar na ajiye saman dirowar gefan gado ya kusance ni sosai cikin taushin harshe ya furta." Ki gaya mini mana menene ba ki so a kira Dr Sailuba kin tabbatar ne?"
Na d'an saki ajiyar zuciya Ina fad'in." Shine na tabbatar tun lokacin da ka fara hasashe tunda kuwa hakane ka ga babu amfanin kiran likita ni ba yarinya ba ce. "
Ina rufe bakina ya zame kasan kafet sujuddur Shukur ya yi. Na zuba masa ido yayin da goshinsa yake kasa yana mika godiyarsa ga Allah sai jikina ya yi sanyi sosai anya kuwa ya ta'ba d'okonta da ciki kamar wannan da aka samu yana murna duk lokacin da muka samu ciki amma dai wannan abin ya yi yawa. cikin raina na ji nima ina son cikin da kuma ina addu'a akan Allah Ya cika mana burinmu na samun d'iya mace mu a
sanya mata sunan Hajja Halimatussadiya.

***

To ko da ta dawo sai da ya gama shan 'kamshinsa tukkuna don sai da ta kwanta hud'u da dawowa sannan ya je gidanta kuma kafin ta dawo din na ga ta kira shi a waya ta gaya masa zata dawo ni dai addu'ata Allah Ya sa kada ya gaya mata cewar ba shine ya bata kudin ba ni ce don nasan ba 'karamin aikinsa ba.
Sati biyu ya kara akan dawowarta ya tafi Legos domin daman dawowartata ce ta sanya shi jinkirta tafiyar ya tabbatar mini da cewar ba zai wuce wata biyu ba zai dawo.
Tunda ta dawo bamu hadu ba dama can tunda aka raba mana gida ita ce mai shigo mini bana zuwa gidanta sai da dalili mai karfi zuwana biyu kacal lokacin da ya yi ciwo da lokacin da ta yi 'barin ciki. Sai dai duk ranar juma'a nakan ce da yaran su je su gaisheta suka dan zauna a can dalili Ladidi mai aikinta na hillatarsu da tatsuniya da labarin kanzon kurage su  kuma akwai son haka idan sun dawo gida suce mama ta ce a gaisheki.
Hadiza kam takan zo mini sa'i da lokaci mu yini tare tunda tare suka tafi da Sukairaju itama cikin kad'aici take hakan ya sanya nake tura mata yaran ranar alhamis bayan sun dawo daga boko sai Masa'udu ya kai su idan sun dan jima ya je ya d'auko su.
Cikin wannan yanayin Nabila ta fito tare suka zo mini ita da Nusaiba wai sallama ta zo yi mini za ta koma jos da zama dalilin abinda ya samu rayuwarta duk abinda ta mallaka ya salwance da kyar Allah Ya bayyana gaskiyar cewar babu hannunta akan abinda ya faru.
Wallahi ta ba nii tausayi sosai ta yi wani irin baki fatar nan da aka kwailayeta ta toye ta yi dabbara-dabbara daka gani ta k'are mata babu kud'in cin abinci ma balle na sayan man bleaching duk wannan gayun babu shi ta susuce ma gabad'aya.
Rayuwa kenan shiyasa duk abinda mutum zai yi ya sanya tsoron Allah a ciki. Kasuwanci ba za a tsarkake shi ba ya ki Haram yaki halak ko ta halin kaka sai an yi kud'i tunda an shiga hurumin Ubangiji kuma ai ba za a ga daidai ba.

Wasu daga cikin kayana na tsinto mata masu kyau set biyar na hada mata da mayafai da hijabak sannan na ce lallai za ta ga sakona a kurkusa..
Kafin su tafi kuwa kuka ta yi sosai da sosai tana ta ba ni ha'kuri har na gaza gane hakurin me take ba ni domin dai gabad'aya cikin nadama da danasani take tunda duniya ta yi kuli-kulin kubura da ita.
Bayan kwana biyu da zuwansa kuwa na kira Nusaiba a waya na ce ta turo mini details din Nabilan tana turo mini na sanya mata dubu dari biyu ciki.
Sannan dama ina da lambar wayarta tun farkon haduwarmu lokacin rasuwar Alhaji Amadu muka yi musayar lambar a lokacin jininmu ya hadu domin ni da ita ne muka dinga tiri-tiri da Hajiya Maryam din akan 'kin cin abinci. Kuma bayan Hakan muna d'an gaisawa a wancan lokacin har idan ta yi status na bude na gani idan abin murna na yi mata murna haka zalika idan abin jaje nan ma na jajanta. Katsam na daina ganin status dinta nan na tabbatar da cewa ta yi block dina ne tunda lokacin aure ya kullu tsakanin maigidan da 'yar uwarta sai ta rufe ni, a lokacin abin ya yi ta ba ni mamaki da daure mini kai
Na kira ta muka gaisa na ce ta duba na tura mata sa'ko kamar wadda na bawa miliyan biyu ta dinga yi mini godiya har muryarta tana rawa tsabar kyautar ta yi mata dadi.

***
Lokaci bayan lokaci Kamalu kan kira ni bidiyo call mu jima muna hira yaro ya yi wani girma da wata haiba ta mussaman wata irin nutsuwa da annashuwa nake tsintar kaina a ciki a duk lokacin da nake kallonsa ina kara tahamdi ga Allah madaukakin sarki.

Watansa uku ya dawo kamar yadda ya fad'i lokacin cikina ya shiga wata na biyar amma bai fito ba ya dai bi jikina kwankwaso da breast sun sake girma sai dai Ina jin ciwon mara kafa sa sauransu har gida Dr Sailuba take zuwa ta yi mini awo ta kuma ba ni maganganun da suka da ce. Wai shi a tunaninsa idan ya dawo zai ga ciki ya fito sosai na ce masa cikin bai ma cika wata biyar ba ai bai yarda ba sai ma ya fara zargi babu shi ya rasa sukuni ko kad'an hankalinsa bai kwanta ba sai da dr Sailuba ta yi masa cikakken bayani ya ce a je a yi scanning a ga mai za a haifa tunda nake samun ciki bai fiye matsawa ba yakan ce duk wanda Allah Ya ba shi yana so amma abin mamaki wannan kam yana dawowa ya daga mini hankali dole na shirya Hadiza ta yi mini rakiya domin yin scanning din kamar yadda ya buk'ata Ashe itama tana 'kunshe da nata cikin ban sani ba bayan an gama yi mini aka yi mata cikin ikon Allah ni mace ita namiji satikan cikinta sun haura nawa ta riga ni samu amma dai tsiraranmu kadan ne za ta riga ni haihuwa wata'kila kafin ta yi arba'in na haihu. Sosai na tayata farinciki  domin can baya gidan Alhaji Halilu ta yi ta samun matsalar lalacewar ciki har dai suka rabu bata haihu ba a wannan matakin da muke ciki da shekaru suka fara nisa ko biyu ta samu sai ta godewa Allah.

Mijinta ne ya kai mu bisa bin umarin maigidan shi dai tun a mota yake ta annasuwa ya rasa ina zai sanya rayuwarsa ganin result din cikin matarsa namiji kuma cikin koshin lafiya ita dashi gabad'aya sai suka ba ni tausayi.

Kwanaki goma da yi mini scanning muka tafi umara ni da shi a cewarsa yana da kyau mu je mu yi godiya tare da addu'a akan Allah Ya tabbatar mana da abinda hasashe  domin kuwa komai yana iya canzawa gashi ya jarabtu da son haihuwar 'ya mace mai sunan Mamansa.
Mun yi addu'a sosai wadda ta shafi kowane bangare satin biyu muka dawo gida.
Rayuwar ta cigaba da gurgurawa sannu a hankali ban san dai me yake tsakaninsa da matarsa ba domin tunda ta dawo ba mu had'u ba kunya ta hana ta zuwa inda nake sai dai sakon gaisuwa idan yara sun je. Shi kuma yana ta zagari tsakanin gidana da gidanta duk wadda take da girki zai je ya kwana. Tun bayan dawowarta babu wata matsala da ta sake faruwa yanzu kusan wata shida kenan cikina na da wata bakwai lafiyar Allah nake gudanar da hurd'odina babu nauyi irin nasu Hassan sannan laulayin da na yi ma takaitaccene a farkon samun cikin ne.
Babu wanda ya san ina sa juna biyu tsakanin anti Yagana da Sahura tunda ban gaya musu ba muna dai yin waya sa'i da lokaci.
Sai da Hadiza ta haihu tukkuna da su anti Yagana suka zo yan gidanmu suka fahimta lokacin ma ni kadai nake jin abinda nake ji nakuda ce nake yin ta a tsaitsaye Hadiza ta haifi namiji yaro lafiyayye mai kama da babansa sai ta dinga ba ni sha'awa wallahi ganinta ri'ke da jaririnta lafiya lau tiriri ya kare.
Kayan da Nabila ta had'awa su Hassan a lokacin haihuwarsu sama suna saman maigidan don haka ya ce da Sukairaju ya zo ya kwashe su suyi amfani da shi ya samu takwara domin kuwa kwana biyu da haihuwarsa ubansa ya yi masa hud'uba da Tajuden.
Yan gidanmu kaf sun halarci taron sunan Hadiza da yamma sai ga Hauwa da leda cike da kayan baby wai ai ta ji an ce yaro ya ci sunan maigidanta. Ta sake ana ta wasa da dariya da ita babu kuma wanda ya nuna mata komai ni kaina janta nake yi da hira yadda ta saki jikinta sosai ya tabbatar mini da cewa ba ta fahimci halin da nake ciki ba ni ma, ko da yake a zaune nake ba lallai ne ta gane komai ba.
Sai daf da magriba ta yi mana sallama ta tafi anti Yagana ta ce da Fati ta zazzage kayan da ta kawo a duba tsaf kada ta kunso wata jarabar ne. Na dinga dariya ina fad'in anti Yagana kenan.
Set din kayan jariri ne uku da turaruka masu tsada da wani takalmi mai ban sha'awa bayan mun gama gani Fati ta had'a kayan ta mayar da su cikin leda.
Sati biyu suka ce za su yi kafin su tafi anti Yagana kuma ta ce kwana biyu kacal za ta kara ta kama hanyar gidanta na yi na yi da ita itama ta zauna ta huta sosai kamar yadda su Fati suka zauna ta ce ai ita babba ce da kunya kada lalacewar ta yi yawa mazajenmu su daina ganin girmanta. Na ci dariyata kuwa na 'koshi mussaman da na tuna yadda suke yin wasan 'buya da maigidan tun musayar yawun da suka yi akan kamfani shi yana jin kunyanta itama tana jin nauyinsa.

Wannan littafin na kudi ne kada ki karanta ba tare da kin biyani hakkina ba.

Aikuwa bayan tafiyarta da kwana biyar ciwon nakuda ya kama ni a gida ranar juma'a kaf kowa yana nan har yaran kuma da safe ciwon ya tashi ban fito daga d'aki ba na kira Dr Sailuba saboda dama tuntuni na yi nak'udata a tsaitsaya don haka zuwanta da minti ashirin da biyar na haihu lafiya lau yarinya mace ta dinga tsalla ihu da ya fargar da kowa Yara suka ki'dime suna murna Mama ta haihu Khalil ne ya ruga gidan Mamansa twin's kuma suka hau sama wajan Babansu bacci yake yi suka tashe shi da ihun murna Mama ta haihu.

Dr Sailuba ba ta bud'e d'aki ba kuwa sai da ta kammala komai ta gyara ko'ina amma still kusan awa guda da haihuwar yarinyar kuka take tsalawa har dai abin ya fara ta'ba ni na fara tambayarta anya lafiya ta ce mini lafiya lau don karon farko bata tsammaci matsala ba.

Tana bude d'akin suka dinga shigowa yan gidanmu su Fati da Hauwa da take jan kafa tsabar k'aduwa da tashin hankali kamar wadda ta yi targad'e a kafarta kallon farko da na yi mata na gane lallai akwai matsala domin duk yadda ta kai ga ganin ta gayyato dariya da annashuwa tasirin damuwar da ta tsinci a kanta a ciki ya danne abinda take kokarin gayyotowa duk wanda ya lura da ita zai gane cewa lallai a rikice take domin kayan bacci ne a jikinta da hijabin sallah.

Bakin kowa kamar audiga tun daga kan maigidan zuwa kan masu aiki yaran da 'yan uwanana sai murna da sambara suke yi don ma dai kukan da yarinyar ke tsalawa ya d'an rage karsashi da annashuwar shi ma ya fara tambayar Dr Sailuba babu matsala da confidence d'inta ta ce masa babu wata matsala lafiya ce. Hauwa ta kar'bi babyn hannunsa tana juyyata can kuma ta dan daga mata idanuwanta tana gwalesu sosai ta dubi ta d'aga rigar jikinta tana tatta'ba jikinta da hannunta sai ta dubi

Dr Sailuba tana fad'in." Ki duba sosai Dr kada ki dinga yin abu daka yarinyar nan bata da lafiya."

A d'an sanyaye ta kar'beta daga hannunta har zuwa lokacin kukan take tsalawa ta dan jima tana jujjuyata

Kafin ta dube ni da sanyi jiki ta furta." Za mu je asibiti domin dubata sosai kukan ya d'an so ya yi yawa sannan jikinta ya d'auki zafi akwai abinda nake zargi."

Gabad'aya ni da shi sai jikinmu ya yi sanyi muka dubi juna.

Ya yi saurin kar'be babyn tana tsala ihu ya d'an dubi Hauwa dake tsaye a gefansa itama shi take kallo karaf ta ce." Ku je asibitin sai a dubata gaskiya bata da lafiya." Na ga sanda ya wurga mata wata muguwar harara ya kawar da kansa cikin wani masifaffan yanayi da tashin hankali.

A takaice dai a ranar a asibiti muka kwana domin dai gado aka ba mu babban likita ya bincike mana ita tsaf sikila ce dole akwai buk'atar zamanmu a asibiti na wani lokaci domin kula da ita.

Tashin hankali wanda ba a sa masa rana. A daran ni da shi kuka domin dai da farko har na fi shi dauriya na dinga tausarsa da kawo masa misalai tare da gaya masa kada ya butulcewa Allah kada kuma ya nuna Allah bai yi masa daidai ba. Ya kasa jurewa hawaye yake d'igarwa domin dai bayanin da likitan ya yi mata babyn sikila ce sosai.  Hauwa kuwa ta kira shi a daran sm da kyar na bashi baki ya d'auka don gabad'aya ba shi cikin hayyacinsa ban ji me take gaya masa ba sai gani na yi ya tashi tsaye jikinsa na wani irin kyarma yana ce wa." Ba ki kunya da nauyin gaya mini wannan maganar ba Hauwa." Itama na ji ta cikin 'karaji tana fad'in." In sha Allahu rabbi sai ta mutu da izinin Allah hakkina ba zai barka ba wallahi ba zan daina mi'ka kukana ga Ubangiji ba ai ba cikin haihuwar ne ba ni dashi ba ni ma, yarinya kuma nafad'a maririciya kuma mutuwa suke yi  kada ma ku sanya rai a kanta domin mun ga haka ya fi sau d'ari.
Jikinsa ya cigaba  kyarma da wata kaurarriyar muryar da ban san shi da ita ba ya furta." Ina ce sai ina auranki tukkuna zan kwanta dake ki samu cikin da za ki haihu shikkenan na sake ki Hauwa saki biyu babu wata dangantaka ta aure a tsakanina dake yanzu na sake ki saki biyu.........
Innalillahi wa'ina ilaihi raji'un!

*A kar'ba da ha'kuri don Allah  hakan tana iya faruwa da rayuwarsu ina fatan dai ba ku mance tushen labari ba. Sakon littafin gudun aure ya isa saura k'arashe in sha Allahu Ina mutukar godiya....*
*GARKUWAR MATA.✍*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *PAID BOOK VIP 1K ON TALGRAM WHAT'S APP GRUOP KUMA #700 VIA 0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*V-VIP AREWAPEN*
*07084653262*
*176*
Na ji komai da kunne na babu buk'atar neman karin bayani ni gabad'aya ma abinda yake gabana lafiyar yarinyarta akwai tsananin damuwa da fargaba a ce ka gama goyon ciki da wahalhalunsa ka haife ka fuskanci wani k'alubalan na mussaman sai yanzu gane wannan shine babban dalilin da ya sanya likitoci suke iyakacin bakin kokarinsa wurin ganin sun dakile yawaitar haihuwar yaran da suke d'auke da wannan lalura. Doke ce a yanzu waliyya da mahukunta basa d'aura aure sai da shedar daidaituwar jini mussaman ga saurayi da budurwar da ba su ta'ba haihuwa ba akansu dai wannan dokar ta fi tsananta akwai sau'ki akan namijin da yake da iyali da kuma bazawarar da ta haihu a wani wajen tana da yara maslaha ce a tsakaninsu ko da suñ yi aure sai su d'auki matakin gujewa samun ciki. Duk da yake duk tsumi da dabara ba a isa a yi wa Allah wayo ba wahalar dai da tiri-tirin shine abin gudu. Na haihu ina murna ban ta'ba tunanin zan sake haihuwar sikila ba ganin na jera haihuwa har sau biyu lafiyarsu lau gabad'aya ni da shi tunda aka samu cikin yarinyar nan ba mu ta'ba zama mun tattauna mas'alar da za ta iya kasancewa a rayuwarmu ba saboda duka tunaninmu daya wata'kila Allah ya d'auke mana tunda mun yi sau biyu a jere dukkaninsu lafiya lau.

Sanin gaibu sai Allah kuma duk abinda ya tsara shine daidai kuma dole a yi godiya gare shi. Lamarin Hauwa kuwa gabad'aya kaina ya kulle na gaza kuma na yi rauni akanta domin duk kaifin tunanina k'wakwalwata ta kasa hakaito mini a wane mizani zan ajiyeta a bayyane komai yake bata da abokiyar gaba sai ni kuma a duk lokacin da sarki Allah ya bata sa'a a kaina don ta d'auki makami ba wani abu ne.
Asibitin na mussaman ne don haka da gari waye Baba Tabawa kawai na ce masa a kawo mini na kuma kira Fati a waya na ce ta had'a mini kaya da duk abinda zan buk'ata tunda ba su tafi ba suna nan likitan dake tsaye kan yarinyar ya bada tabbacin kan cewa a k'alla mu yi sati ko kwana goma kuma alhamdulillahi kwana daya kacal da muka yi yarinyar ta sassauta kukan da take yi zafin da jikinta yake d'auka ma ya yi sau'ki ta kuma samu bacci. Hakan ya sanya shi tafiya gida domin yin wanka tunda tare muka kwana cikin tararrabi da zullumin abubuwa masu yawa ya dinga ba ni tausayi daga zarar na daga kaina na dube shi hakika Allah ba yadda baya aiwatar da ikonsa a kan bayinsa. Ya yi addu'a akan samun haihuwa kuma diya mace wadda ya nema a wurin Allah Ya amsa masa sai kuma ta zo a maririya mai rangwamin lafiya wannan ma jarabawa ce me zaman kanta amma godiya ga Allah itake nuna cikar munini tunda ai akwai ma'auranta da duka yaran nasu suke kasancewa da cutuka mabambamta kuma daya bayan d'aya ya d'aukesu su koma gare shi bayan iyayen sun sanya rai kuma ba su gaza ba wurin nemo musu magani da kudi da lafiyar jikinsu. Ubangiji ta kowace suffa ya kan jarrabi bayinsa wanda yake so domin auna imaninsu. Da wad'annan nasihun na d'an samu kansa amma ko bayan wannan nasan damuwar ai tana jika dalilin abinda Hauwa ta yi tamkar ba jininsa ba k'iyayyar ta munana ta kuma tsananta Allah ne mai rayawa kuma shine mai kashewa shi ya ba mu don ya kar'ba ai ba mu da abinda za mu yi tunda mu da muke zaune a duniyar zaman jiranta muke yi. Wannan shine kawai abinda na bari a zuciyata maganganun Hauwa akan yarinyata ba su razanar da ni ba, musulmace ni dole kuma na yarda da kaddara mai kyau ko mara kyau. Haihuwa ya ba ni ya sake ba ni ya ba ni ta mussaman wadda ba kowa ke da baiwar ba har sau biyu masu lafiya rayayyu guda shida yana kuma raya mini su cikin aminci da kulawarsa da kuma tarbiyarsa babu abinda zan ce da shi sai godiya kuma duk abinda ya zartar daidai ne.
Da Baba Tabawa muka kasance a asibitin tunda gaskiya akwai tsaro sosai ba su barin wannan shige da ficen itama saboda maigidan sananne ne yana kuma da alfarma ya sanya suka barta ta zauna. Alhamdulillahi cikin kwanaki hud'u abubuwa sun yi sau'ki ta daina duk abinda take yi tana kuma kama nono ta sha cikin nutsuwa ta yi baccinta da kwanciyar hankali. Muka samu nutsuwa ni da shi mussaman da likitan yake jaddada mana cewa muddin an kula an kiyaye komai kan ka'ida ciwon ba zai dinga motsa mata ba a kai-kai.
Kwananmu takwas muka dawo gida. Ya zama kamar kufai shiru babu hada-hada ta yara duk suna ma makaranta masu aiki Mairo da Taburni na kicin Hassan da Usaini na bacci bayan wankan da aka yi musu shi kuma Sultan na tare da su a kicin.

Na kira Hadiza a waya na gaya mata na dawo cikin kasa da minti ashirin sai gasu gabad'ayansu suka kewayeni duk babu wata annashuwa a tare da su babyn tana ta bacci babu halin d'aukarta domin dai likitanta ya bada umarni hakan kada a yawaita jagwalgwala mata jiki sai dai ido kawai Fati take tambayata da wane suna za a dinga kiranta tunda wai Sukairaju ya gaya musu sunan Hajja ne da ita na ce Mufida haka babanta ya ce a kira ta.
Yini muka yi tare da su har yaran suka dawo daga makaranta ganina a gidan ya sanya su shiga tsananin murna hankalinsu gabad'aya nakan babyn sai sun d'auketa Minal har da kuka sai da na kira Mairo tukkuna na ce ta ja ta su fita domin wani irin ciwon kai nake yi  kukan da take yi kuma yana sa'bata da yanayin yadda duk na gansu cikin damuwa mussaman Khalil duk jikinsa ya yi sanyi na kasa gane shin akan menene  ba ni tsammanin ubansa ya gaya masa ya saki uwarsa sai dai idan ita za ta gaya masa kuma ba na tsammanin ta tafi tana gidanta tunda na ji lokacin da yake magana da Mairo yana gaya mata sakon Ladidi tunda k'awarta ce idan Hauwan ta aikota sukan dan jima suna  hira akwai wani k'aramin gari a cikin bauchi mai suna giayade anan cibiyar iyayensu take duk da ba su had'a wata dangantaka ba hirar yau da gobe ta sanya suka fahimci garinsu daya.
Washe garin ranar da muka fito Hajja da yayarsa suka dira dama ya gaya mini shine ya dakatar da su tunda ko sun zo muna asibiti ganin hakan ya sanya ni ma na hana anti Yagana zuwa tukkuna can gidanmu ma haka na gayawa Babanmu a waya cewa su bari sai mun fito Sahura kuwa kusan kullum sai mun yi waya.
Sai dare tukkuna muka samu ke'bewa Hajja fadi take yi Hauwa abinda ta yi muku Amina Allah Ya yi mata ba zan yi mata baki ba ba kuma zan nunawa duniya Tajo ne nawa ba amma da wahala ta sake yin katari da namiji da abokiyar zama kamarki zahiri kin yi iyakacin bakin kokarinki wurin ganin kin kawo daidaito a tsakaninku kin yi bajinta kwarai kuma kin yi da jiki da aljihunki a tarihi ban ta'ba ganin kishiya irinki ba Allah ya biya ki da aljanna Ubangiji Allah Ya dubi rayuwarki. Wad'annan yara kuma ina yi miki addu'a akan Allah Ya ba ki wuyan d'auka Allah Ya raya mana su.
Na dinga amsawa da Amin Amin amma bayan haka ban iya furta komai ba akan abinda suke tattaunawa Hajiya Saratu tana ta fad'a akan zaman da take yi tunda an yi ta ta kare babu wata sauran igiya zaman me take yi kuma har tana fad'in da safe za ta je gidan ta ji dalili babu sauran wani mutunci da zumunci a tsakaninsu tunda har ta iya rufe idonta  ta yi wa dan uwanta wannan cin fuskarsa. Gaskiya ne a wannan ga'bar takai-takai kawai ake yi kowa nasa ya sani domin kuwa abinda ita Inna Uwanin ta nuna kenan. Wannan karon Hajja ta saki ragamar hannun yaranta ai kuma magana ta 'kare babu sauran gyara babu amfanin zamanta a gidan ta kama hanya ta tafi yara kuma ta bar su a gidan ubansu.
Da wannan suka rufe maganar ni dai magana akan Hauwa ta k'are a bakina domin ban san abinda zan ce ba ta gama goge mini hadda ta tilawa.
Aikuwa kamar yadda ta kwana da al'amarin garin Allah Yana waye wa ko karyawa ba ta yi ba ta nufi gidan Hauwa. Ni dai Ina d'aki da yake kofar a bud'e take saboda yaran sun shigo mini kafin su tafi skull na ji fad'anta a falo

har ina tsinkayar muryar maigidan. Fadi take yi zaman nata ai bashi da wani amfani ban kuma yarda da abinda ta fad'a ba wai juna biyu gareta ko za ta tafi sai a bari ta haihu tukkuna shin kai ka san cikin ne da ita. Cikin rashin karfin sauti na ji maganarsa amma ban ji abinda yake cewa ba. Na yi zuru ina mamaki cikin da take ta ha'kilo a kansa shin tasan dama tana dashi ta yi wannan rashin mutuncin ko kuma dai karya take yi don kada ta tafi ne. Wani sashi na zuciyata ya dinga gaya mini karya take yi da tana da ciki da kowa ya sani tunda abinda take nema ne kenan kuma ba zata zafafa bakincikinta ba.
Can wajan minti ashirin da biyar a tsakani na dinga jin kuka kasa k'asa da maganganu suna tashi sai da na kasa kunne tukkuna na gane muryar Hauwan ce take wani irin kuka mai cin rai Hajja tana ta yi mata magana akan ta yi shiru amma sai kara karfin kukan take yi. Cikin babban sauti na ji muryar Hajiya Saratu tana cewa kan ki kika tonawa asiri Hauwa ba mu za'bi Amina ba saboda muna 'kin ki. Mun za'bi kyawawan halayenta ne da kuma biyayya amma tunda yanzu magana ta kare babu buk'atar a yi ta maimaitawa sai dai addu'ar Allah Ya fitar da sakamako da gaggawa a tsakaninku wanda ya cuci wani sai Allah ya saka masa ba mu da wata hanyar gyara kuma babu wata mazahaba da za a bi saki ukun ai ba a lokacin daya ya yi miki su ba an yi daya da farko ya zo ya maimaita miki biyu saboda haka baki fara yin nadama ba Hauwa kuma muna nan ba za mu fasa addu'a ba idan shi ya cutar dake kamar yadda kike yawaita fadi Allah Ya saka miki.
Saboda irin bud'e wutar da Hajiya Saratu ta yi a gidan sanya kowa jikinsa ya yi sanyi masu aiki kaf ba su fito ba domin sun jima a falon suna musayar yawu tana ta jaddada mata 15m din da take tunanin maigidan ne ya bata to ba shi ba ne ni ce hakan ya kara tsananta kukanta ina daga d'aki ina Jin gurnaninta cikin tashin hankali kamar wadda ke shirin tayar da sarkin aljannu.
Shi gabad'aya ma bai sauko ba balle ya tanka takaici da b'akinciki ya na ta nukurkusarsa. Babu arziki Hauwa ta kama hanyar garinsu jin zafafan kalamai raddi masu kauri da jefa zuciya cikin rud'ani
da bala'in yanayin da ba zai misaltu ba dama aka ce duk wanda ya ce tukunyar wani ba zata tafasa ba tabbas ta shi ko d'umi ba za ta yi ba.
Washe gari Nusaiba ta zo mini da yaranta kaf muka yini tare su kuma su Fati suna jiran zuwan anti Yagana tukkuna don ba su kai ga tafiya ba.
Kwana biyu a tsakani ta iso da yamma kuma matan gidanmu gabad'ayansu har da Babanmu da Baba Sule suka kwana da yamma suka yi shirin tafiya gabad'aya amma ban da anti Yagana saboda na ce ta bari tukkuna sai nan da sati d'aya
Yaran shop's dina har da securities din dake gadi a wajan Lawan ya jagorancesu a daran da su Fati suka tafi muka jima da suma muna tattauna cigaban da ake samu koyaushe.
Haka na dinga samun baki daga wannan sun tafi wasu za su zo Sahura ita kadai ta zo mini wannan karon Yusura ta sake samun ciki sai kawai na ganta da yarinya jale-jale tana koyar tafiya yarinyar Idiris ce uwarta ta cire ta daga nono lokacinta bai cika ba ta yi aure a cewarta baya kawo kudin abincinta

iyayanta suka ce ta cire ta daga nono a kai masa 'yarsa suka kawota suka dire babu Imani uwar ta tafi ta yi aure. Mai shegen k'iwa da rashin yarda saboda tsabar bala'i  lallai Sahurar ba zata huta ba ko uban da ya haifeta bata yarda dashi balle danginsa ta ma'kale mata na dinga mamakin wannan lamari kwatankwancin abinda Minal take yi mini yanzu ko wurin aiki da ita take zuwa Hajja kuwa sai 'kara mata karfin gwiwa take yi tana fad'in kada ki sare kada ki gaji wata'kila zata ji kan ki da d'a da dukiya ba a yi musu mugunta.
Muna tare da su tsayin kwanaki uku babu irin batutuwan da ba mu tattauna ba abinda Hauwa kuwa ta aikata ya yi bala'in ba su mamaki amma jin irin hukuncin da maigidan ya yanke a kanta ya sanya zuciyoyinsu suka yi sanyi.
A ranar da suka shirya tafiya wasu bakin suka dira Hamusu da Usaini kowanne da iyalinsa sai kuma Yusi da Saminu. Hajja kuwa ta samu 'kawa 'yar gidan Usaini mai sunana kenan itama suna kiranta da Minal ta dinga tsokanarta da faratu haske ne da ita kau har ta so ta fi ubanta haske Hajiya Saratu na tsokanar Hajara kamar ba goyonta ba, ita yarinyar ashe mahaifiyar Ummansu Saminu ta d'auko  domin duka hasken fatar ta gada musu duk da ta tsufa amma tana nan kar kar da ita Fulani ne na asali.
Kwana biyu da zuwansu Yusi yake gaya mini Kamalu daf yake da dawowa gida domin sun yi magana da shi a cikin satin da ya wuce na ce bai gaya mini ba duk da kuma mun yi magana da shi kwana hud'u da suka wuce ya dai tabbatar mini da cewa daf yake da ya kammala abinda ya kai shi amma bai fada mini ranar da zai dawo ba, amma ba na mamakin  kan cewa ya sanar da maigidan tunda kusan ya fi sakewa da shi fiye da ni.
 Kwanaki biyu a tsakani suka tafi Hajiya Saratu ma ta riga Hajja yin gaba domin ta ce ita zata zauna ta kwana biyu tukkuna har na ji Yusi yana tsokanarta  wai sai ta taso sun tafi haka yake janta da tsokana irin wadda ma bai yi wa Gwaggo irinta ba tsakanin Yusi da Hajja akwai amana da kuma 'kaunar juna har da rantsuwa wai gidan babu dad'i idan bata nan ta ce masa ba wasu kwanaki za ta yi da masu yawa ba. Shi kam babu halin zama makaranta ga kasuwa ba ma shi da ishashen lokaci na kansa.
Hajja ta sake sosai da jikokinta tana jan su a jiki da wasa da dariya har dai suka sake tunda sun gano cewar kakarsu ce wadda ta haifi Babansu idan suna gidan karad'insu kad'ai ake ji a falo tana ta biye musu Baba Tabawa na yi musu dariya. Minal ce take ma'kale da ni da Mufida suna dawowa daga makaranta a wasu lukutan ko uniform ba ta zuwa ta cire za ta same ni a d'aki ta'ba nan ta'ba can ta yi ta han'koro ita lallai sai na bata k'anwarta. Cikinsu har khalil babu wanda ya taba daukarta sai dai gani daga nesa Babansu ya ce ko za a ba su sai ta kara wayo tunda ga abinda likita ya ce kuma alhamdulillahi ta yi lafiya tana shan nono sosai ta yi baccinta na rana da dare babu kuka mai zaburarwa sai dai tak'aitacce dalili duk wasu sharad'ai ina bi yadda muka yanke ni dashi rainonta yana hannuna duk rintsi babu buk'atar taimakon masu aiki gudun yin abinda zai  sa'ba da lafiyarta.
Yau kwananmu talatin da tara ya kama saura kwana daya kacal mu yi arba'in ina toilet na din ga jin kukanta a gaggauce na fito da sauri na riski Minal kane-kane saman gado tana ta cakumarta da wannan rawar kan nata. Tsawa

na yi mata irin wadda ban ta'ba yi mata irinta ba ta kuwa zabura da sauri ta juyo tana kallona wanda ya yi daidai da shigowar Khalil na cigaba da Fadin." Ba ki jin magana ko, na ce ki bari zan baki ita ba yanzu ba tukkuna."
Ta cire hannunta da sauri daga kan towel din Khalil da sauri ya dube ni yana fad'in." Mama me ta yi mata?"
Shiru na yi ban ce masa komai saboda kwanaki ya daketa akan haka alokacin da ta taba yun'kurin aikata abinda ta yi a yanzu. Na nufi yarinyar da sauri na dauketa aka ci sa'a kuwa ta yi shiru tana lumshe idonta baccin za ta koma.
Ita kuma ta sauka daga gadon tana ra'be-ra'be tana kallon Yayan nasu na kalleshi ina fad'in kada ka daket....ban kai ga rufe bakina ba ya kwada mata wani mari ta kwallara kara a ki'dime ta yo wajena. Na rufe shi da fada sosai. Ya fara fadin." Mama yarinyar nan sai ana dukanta fa wallahi rawar kanta ya yi yawa haka ta ga 'yan uwanta na yi tuntuni ake fad'in magana d'aya amma ta'ki ji ta zo ta cakumeta alhalin ba ta da lafiya."
Na sassauta sosai ina fadin." To na ji amma dukan da ka yi mata ya yi yawa kada ka sake ka ji ko?"
Ya gyad'a kansa yana sauke numfashi ita kuma dadi take yi." Mama ki yi hakuri." Na ce na ha'kura ai amma kada ki sake."
Ta daga mini kanta tana jan hanci. Da gaske ta sangarce shekara tara fa yanzu ya kamata ace ta rage lalata shi kuma yanzu jin sa yake yi babba a cikinsu duk wadda ta yi shirme zare idonsa yake yi bai dai ta'ba dukan su Hassana ba sai dai muzurai da tsawa idan ya ga sun yi abinda bai da ce ba.
Ya nuna mata hanyar fita da hannu ta gane abinda yake nufi aikuwa sumi sumi ta fita. Na ce Kai ba ka jin tsoro ta gayawa babanku kasan 'yar gaban goshi ce. Ya d'an yi murmushi yana fad'in ai Mufida ta ture mata fada yanzu itace akan karagar mulki."
Takaitaciyyar dariya kawai na yi na cigaba da jijjiga yarinyar a hannuna.

kada ki karanta mini littafi ba tare da kin biya ni hakkina ba.

Ya zauna kusa da ni a nutse zamansa ya sanya ni nazarinsa sosai yana da damuwa tuntuni na fahimta kawai shiru na yi.
Ya ce." Mama ko zan iya sanin abinda ya shiga tsakin Mamanmu da Baba don Allah ki gaya mini da na tambayi Hajja ta ce mini babu sauran zama a tsakaninsu ma'ana babu damar da za a gyara ta dawo, ki yi hakuri don Allah ki sanar da ni rufe mini bashi da amfani mahaifiyata ce na yarda amma k'wakwalwata ba zata manta da abubuwan da suka dinga faruwa ba tun da k'ananun shekaruna na gane dabi'unta ba su da kyau na yi iyakacin bakin kokarina wajan ganin ta gyara an zauna lafiya amma hakan bai samu ba.
Jikina ne ya mutu da jin abinda yaron ya zo mini da shi. Yaro karami da tunanin manya idan yana manyance abin har mamaki yake ba ni wallahi sai na yi saurin yin kasa da kaina
To na ce masa me in banda abin Khalil Hajja ta sakaye masa saboda abu ne mai muni a ce ya ji abinda uwarsa ta aikata. Amsar ai tana wajan Babansu tunda shi ya aikata ba ni da abinda zan ce.

Ya gaji da magiyarsa ya tashi ya tafi domin abinda nake nanata masa shine ni ma ban san komai ba.

BAYAN WATA UKU
Bauci
"To tunda kina ganin akwai yiwuwar haka sai ki jarraba ki gani ni dai ba ni da wata dama yanzu Hauwa gabad'aya ma cikin nadama nake a halin yanzu dalili ban san da wace fuska zan kalli yar uwata ba abinda ki ka aikata bai yi mini dadi ba ko kad'an gashi saboda ke sakarai ce kin dawo gida hannu rabbana in banda wannan kudin da ya baki wattanin baya ina takardar kamfanin da kike ta masifa akan ba kya so kun rabu rabuwa ta har abada babu kome kamfani kuma yana hannunsa har yanzu tunda dai bai baki shedar mallaka ba kin yi a banza sakarai shashasha duk shawarwarin da k'awaye da abokan arziki suke ba ki kin watsar kowa ya gaya miki ta wannan hanyar ake ya'kin kwatar 'yanci a gidan miji shikkenan ai sai mu zauna ni dake ai mu tsotsi tsamiya kin raba da ni da 'yar uwata
Hauwa gashi abinda duk muke han'koro bamu samu ba idan kun yi auran kisan wuta kin biya wanda za ku kulla yarjejeniyar shin kina da tabbacin zai sake ki, ki koma gidan Tajo. Shi din ai ba mahaukaciya ce ta haife shi ba, ta wace hanyar za mu bi koda hakan ta kasance muga bu'katarmu ta biya?" Inna Uwani ta kai k'arshen maganarta cike da damuwa mai tsananin gaske.
Ta nisa yayin da take ko'karin korar damuwa da wasi-wasin zuciyarta ta ce ." Zai yiwu Inna don mun gama magana da Yaya Naziru mijin Sadiya na ce zan bashi miliyan uku idan mun yi aure wata biyu zuwa uku sai mu rabu. Maganar komawa dakina ai mai sau'ki ne in sha Allahu zan koma kuma zan yi kokarin ganin na gyara na zauna lafiya da ita da shi don yanzu gabad'aya hankalina na gidan da yarana shikkenan Amina ta zama ita kad'ai yaran ma sun zama nata saboda na riga nasan na yi sallama da yarana Inna kamar fa ba ni na haifesu ba."
Sai hawaye shaaaa! suka fara kasa tsare a kumatunta. Ta takure jikinta sosai ta jingina bayanta jikin wata tsohuwar kujera dake falon nasu tana kuka mai tsuma zuciya.
Ta ce." Hauwa ba ki da kunya da ta ido yanzu Nazirun za ki aura da wane idon za ki dubi Sadiya duk abinda za ki yi fa ki yi tunani akai shima Nazirun kwad'ayin me yake yi ne, ki je ki nemi wani a waje wanda babu dangantaka mana.
Ta dago kanta tana kallonta kafin ta ce." Shine kawai nake ganin zai cika alkawari Inna tunda ai rashin ba shi goyon baya ne a wancan lokacin ya sanya ya nemi auran Sadiya Inna kada ki manta fa tsohon saurayina ne. Kuma ya gaya mini kudin nan da zan bashi zai dora akan kasuwancinsa da ya yi rauni tunda zahiri yanzu Sadiya ta fi shi samu tana aiki tana kuma business ni kaina na sha yin order a wajanta.
Ta ce." Saboda baki da wayo ko, ba ki tunanin d'adin baki ya yi miki domin ya rama abinda ki ka yi masa a baya wane irin cin kashi ne ba ki yi masa ba da k'yamata saboda ba shi da kud'i, ki yi nazari sosai akan hakan."

Shiru ta yi na d'an wani lokaci kafin ta ce." Inna ki daina wannan tunanin don Allah shi kansa fa dana gaya masa kudirina goyon baya ya ba ni ya ce yana da kyau na yi kokarin ganin na koma hannun uban yarana har yana jaddada mini cewa idan ba tsautsayi ba babu wani dalilin da zai sanya shi rabuwa da matarsa saboda rayuwar yara na shiga garari."
Inna Uwani ta dinga galla mata harara kafin ta ja tsaki ta furta." Ke har wani shiga garari kike hangowa yaran da suke da uba irin Alhaji Tajo. Suke kuma da uwar riko irin Amina. Wannan ba hujja ba ce amma tunda kin ce haka ba zan hana ki ba wata'kila gaskiya ne yana buk'atar kudin ne domin d'orawa akan kasuwancinsa tunda har ya amsa tayin da ki ka yi masa sai ku yi abin a sirrin ce yadda babu wanda zai gane da wata manufar kuka shirya auran...........✍
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*
[6/4, 3:03 PM] Hauwa Galadima: *□ ALHAMDULILLAHI*
*177*
*SADAUKARWA GA IYAYAN DA ALLAH YA JARABTA DA FITINANNUN YARA IYAYEN DA ALLAH YA JARABTA DA HAIHUWAR YARA MASU DAUKE DA LALURAR JINI SIKILA. SADAUKARWA GA JAJURTATTUN MATAN DA SUKA YARDA DA RUSHEWAR FARINCIKI SU DOMIN JIN DADIN YARANSU. SADAUKARWA GA MAZAN DA SUKE HAKURI DA JIMIRIN RIKON MARAYA. SADAUKARWA GA ILAHIRIN MASOYA MAGOYA BAYANA WANDA NA SANI DA WANDA BAN SANI BA BINTA NA GODIYA NA SAKE GODIYA ALLAH YA SAKA DA ALHERI LITTAFIN GUDUN AURE BIYU NE A MADADIN DAYA DOMIN YA YI MUTUKAR TSAYI SOSAI YA ZAMA COMPLETE A TELEGRAM 2K DOMIN SAMUN DAMAR KARANTA SHI*
*0542382124...BINTA UMAR GTBANK*
*07084653262*
*177*
Wannan shine tunanin Hauwa wanda babu technology ko kad'an a cikinsa. Lokacin da maganar ta fasu a cikin danginsu sun yi mamaki da k'ananun maganganu amma ganin yadda Sadiya ta goyu da bayan auran ya sanya kowa bakinsa ya mutu. Ita kanta Hauwan ta yi mamaki sosai amma da ta tuna cewa auran kwangila ne sai hankalinta ya kwanta ta fara tunanin ko mijin nata ya gaya mata yadda suka shirya wata uku kacal za su yi su rabu. Gabad'aya lokacin idonta ya gama rufewa babu abinda take da buri illah a dauran auran wattani uku suka cika ya saketa kamar yadda suka yi alkawari zuciyarta bata ta'ba yi mata kokwanton wani lamari zai iya kasancewa ba.

Ba mu da labari daka ni har maigidan sai saura kwanaki biyu d'aurin auran Hajja ta kira shi a waya muna tare a dakinsa take gaya masa Hauwa za ta yi aure Inna Uwani ta kira tana gaya mata nan da kwana biyu za a d'aurin auran. Bai shiga wata wata damuwa ba ya yi fatan alheri suka d'an ta'ba hira kad'an kafin su yi sallama ya kashe wayarsa.
Na d'auka zai d'an nuna kishinsa ko yayane tunda sautari wasu mazan sun tsani su saki mace su ji da gaggawa ta yi aure duk da nasan babu wata soyayyar kirki a tsakaninsu amma ai sun haihu zai d'an ji wani iri sai kawai

ma na ga ya d'auki Mufida yana yi mata wasa yarinyar ta yi gwa'bi babu lefi amma dai da mutukar bambanci a hallita a tsakaninta da yan uwanta tun bayan haihuwarta sau biyu kacal ciwon ya motsa mata dalili muna mugun kiyayewa da bin ka'ida cikin kowane yanayi koyaushe tana hannuna na ri'ke na goya idan ta kama. Allah Ya jarrabe shi da masifar sonta sosai saboda dalilai bambamta sunan Mamansa sannan kuma 'ya macace mai rauni mai kuma rangwamin lafiya. Zahiri ya so Minal amma kamar yadda Khalil ya fad'a kwanakin baya yanzu dai Mufida ce ke kan karagar mulki don ni kaina idan muna tare bai fiye ba ni lokacinsa ba. Idan ya d'auketa sai su yi ta wasa itama ta yi sabo dashi tana ganinsa za ta dinga mik'a hannunta tana 'bangale baki ga shi kamarsu daya bayan yanayin ciwonta ta kwashi yanayinsa ta kowane sashi mussaman k'aramin jikin shiyasa abin ya yi yawa 'kank'anuwa ce sosai amma dai babu rama ta tashin hankali a jikinta a murmure take.
Na kasance sosai cikin nazari da tunanin auran gaggawar da Hauwa za ta yi k'asa da wata hud'u da mutuwar auranta babu abinda zuciyata ba ta gaya mini ba akan haka. Wani sashi na zuciyata na gaya mini wata'kila ta samu wanda take sone kuma mai wadata da wannan nazarin na yi ko'karin ganin na mantar da kaina lamarinta tunda Ubangiji ya datse alakarmu domin ba ni fatan ta sake dawowa cikin rayuwarta har abada addu'ar da a koyaushe nake yi kenan. Ina ganin status dinta jefe jefi tunda har yanzu muna da serving din lambar juna ban goge ba itama bata goge ba amma ba mu ta'ba yin magana ba idan ta d'ora ma ba ni dubawa saboda har abada ba ni buk'atar abinda zai k'ara had'a ni da ita. Dalilin da ya hana ni goge lambarta kuwa saboda yaranta a duk lokacin da Khalil ya buk'aci magana da ita zan bashi lambar tunda duk tsiya ai ba canzawa towo suna dole itace uwarsu kuma ba zan d'auki aniyar datse alakar da take tsakaninsu ba kamar yadda koyaushe Babansu ke gayawa yaron ko za su je bauci wajenta sai sun girma ba yanzu ba yaron har ya gaji da bibiyar lamarin ya ha'kura abin yana yi masa ciwo ainun yadda ya damu da ganin irin rabuwar da iyayen nasa suka yi wadda duk wanda zai bud'e baki zai gaya masa cewa babu sauran gyara kuma sun karanta karatun a islamiyya.

****

To wani abu da Hauwa ba ta sani ba shine har yanzu Naziru yana sonta dama a rashinta ne ya auri Sadiya tunda a wancan lokacin ta raina samunsa k'aramin 'dan kasuwa ne yana sana'ar sayar da leda a kasuwa da abinda ya danganci buhu da bacco sai dai inda Allah ya taimake shi shagonsa ne ba haya yake yi ba. Kuma ya yi kokarin ganin ya gina gidansa mai d'akuna uku da shago a waje d'aya yake kiwon kaji biyu Sadiya take amfani da su shagon waje kuma yaransa da yake duk maza ne yanzu sun zama samari su hud'u suna amfani da shagon amma dai band'aki d'aya ne duk da shi suke amfani a cikin gidan. Haihuwar da ta yi ne a yanzu ta haifi mace wadda gabad'aya suka d'auki son duniya suka d'ora mata.

D'akin nan da yake kiwon kaji shi ya gyara mata aka yi sabon fenti da sumintin kasa amma dai duk da haka d'akin yana warin kaji tunda ya jima yana kiwon shekara da shekaru d'akin ya game da wari abin sai addu'a.
Ranar da aka d'aura auran ta tare suka kwana a daddafe shi a wajansa hakan ba komai bane tunda ya saba sha'kar warin k'ashin kajin da yake kiwo wanda suka hadu da dusar abicinsu. Ita kam a wajanta sabon lamari ne da take ganin ba za ta iya jura ba mussaman da wata gaisuwar kirki bata ratsa tsakaninta da Sadiya ba da gari ya waye ta yi tafiyarta wajan aiki gidan kaca kaca gashi bashi da wani girma k'udaje sai shagalinsu suke yi daga cikin d'akinta tana iya jiyo zarnin fitsarin samarin gidan da ya had'u da warin masai yake fitar da wata irin k'alla tunda na gargajiya ne. Sai shi da kansa ya zuba ruwa a bokiti ya wanke bandakin tukkuna ta iya shiga ta yi wanka yadda ya nuna ai hakan ba komai ba ne tunda ya riga ya saba Sadiya ba ta yin aikin gida sai ta dawo daga aiki to balle kuma yanzu da take ganin ba ita kad'ai ba ce matar gida. Da wannan matsalar aka fara domin dai rige-rigen shiga band'anki ake yi a gidan samarin yaransu duk nan suke uzurinsu har ma da abokansu idan sun zo wataran ma tana ciki tana uzuri za ta ji ana buga mata kofa wai ta yi sauri ta fito. Yaran da ada can suke ganin girmanta dalilin amincin da yake tsakaninta da Mamansu yanzu ko kallo ba ta ishe su balle su gaisheta. Aka dinga fafata rigima sadiya ta yi duma ta barta da yaran sai rashin kunya suke yi mata ita kuma duk abinda take yi na kasuwancinta bata fasa ba gari yana wayewa za ta tafi aiki ranar hutu kuma ta shiga kasuwa sare sare kayan da take sayarwa.
Sai ya zamana Hauwa ke aikin gida ta yi girkin rana da dare koyaushe idan ta yi masa korafin cewa babu ajadanar haka a shara'din auransu sai ya bita da lallami da dadin baki yana ce mata idan bata saki jikinta ta nuna auran soyayya suke yi ba mutane za su fahimci manufarsu. Hakan ya sanya take gyara gidan har ta yi griki ta kuma wanke bandaki Sadiya na wajan aikinta ta dawo kuma ta d'ibi abinci ta ci ta k'oshi ta yi mata duma kamar babu sanayya a tsakaninsu
Babu wata maganar arziki sai kame-kame sai hakan ya kara tayar mata da hankali gashi tun farkon tarewarta ta bashi dubu dari biyu da hamsin akan ya kama mata haya koyaushe idan ta yi magana sai ya ce mata gidan ne ba a samu ba. Haka ta yi wata biyu a daddafe a gidan lokacin sun yi fito na fito da Sadiya uwarka ubanka sun kuma yi wa kansu tononan silili har Sadiyan na fad'in indai Naziru ne gata nan gashi nan ai ba tomo ba ne kuma ta kama kafar wala tunda duk mazajen da suke gari ta rasa da wanda za ta yi auran kisan wuta sai da mijinta.
Lokacin ne maganar ta fasu a dangi iyayensu maza kowa ya san dalilinta nayin auran kisan wuta don ta koma gidan tsohon mijinta ne. Inna Uwani sai da fita ta gagareta saboda kunya da tashin hankali irin lalataccen kallon da 'yan uwan mijinta ke yi mata sai ta zama abin kallo ma domin
har gida aka dinga zuwa ana yin ala wadai da irin yadda ta bada goyon bayan aikata abinda Allah Ya haramta shi kuma Naziru ya riga ya gayawa mahaifiyarsa cewa bai auri Hauwa don ya saketa ba. Amma kuma ita sai ya ce mata idan har tana so ya saketa sai ta kara masa miliyan biyu kudi sun

kama miliyan biyar da yake hankalinta a tashe yake da barin gidansa babu ja'inja ta kàra masa. Da wannan hanyar ya dinga kar'be mata kudi har sai da ya zama ya tatiketa tsaf kuma ya ce ba zai saketa ba saboda yana sonta dangi kuma kaf suka goya masa baya. Lamarin da ya janyo mata mummunan ciwo jininta ya hau aka dinga tiri-tiri da ita don har kwanciya ta yi a asibiti a lokacin ne muka samu labari ni da shi mun je kano hutu zai d'an gudanar da wani aiki Hajja take gaya mana halin da ake ciki domin dai duk yadda lamarin ke yi mata zafi a ranta sai da ta je har can bauchin ta duba jikin Hauwan ta kuma ce masa lallai ya tura mata da kud'i domin jinyya saboda babu tunda har ya yi rantsuwa akan janye kyautar kamfanin da ya yi mata ya ce babu amfanin mallakawa ma'kiyi abinda zai kawo masa cigaba a rayuwarsa. Mutum ne mai bala'in riko da tsananin gaba do dai yanzu an sake girma amma dai yadda ya'ki jinin Hauwa haka ya'ki jinin mutuwarsa sunanta 'yar ta'adda a wurinsa yana rangwatawa ne kawai saboda Hajja ta nuna tsananta gaba da kiyayyar bashi da amfani tunda an riga an hadu babu yadda za a yi da juna.

To ita ga da niyyar da ta yi aure amma ga yadda kaddarar takasance

A lokacin kuwa ya tura mata da dubu dari biyar ya kuma kira wayarta tun bayan rabuwarsu wata biyar kenan suka gaisa 'kasa k'asa nake yin maganarta tana magana a hankali ya dubata da jiki sosai sannan ya ce ta duba ya tura mata sa'ko. Ya mi'ko mini wayar wai tana son mu gaisa babu yadda na iya haka na kar'ba nasa a kunnena na ji maganarta a raunane kamar ma kuka take yi. Zuciyata ta d'an karye kad'an amma ban bari ta gane ba muka gaisa sosai na yi mata ya jiki ta tambayi yaran gabad'aya har da k'aramarsu Mufida na ce duk nuna nan lafiya lau.

Jin ta yi shiru ya sanya na mik'a masa wayarsa na ji yana gaya mata idan da buk'atar wani taimakon gaggawa ta sanar dashi daga haka ya kashe wayarsa.

Ko da muka keb'e bai bai tashi zancan ba sabgoginsa kawai yake yi cikin kwanciyar hankali da nutsuwa tun kafin mu zo nasan dalilin zuwan tunda bai gaya mini ba ni ma ban nemi jin karin bayani ba Hajja ta kira ni a waya ta gaya mini yana yi wa Kamalu gini amma bata gaya mini wane iri bane shin na gida ne ko kuwa na makaranta.

Sati daya muka yi a kano muka koma abuja cikin yaranmu da suke samun kulawa wurin masu aikin da a yanzu nake ganinsu kamar 'yan uwana saboda yadda sha'kuwarmu da su ta kara tsananta. Babu wani sa'bani da ya sake giftawa tsakanina da shi tun bayan fitar Hauwa muka samu wani irin daidaito da kara kusanci ga juna gabad'aya hankali da tunaninnmu yana kan yaranmu mussaman ita wannan din da muka samu daga baya. Ban ta'ba jin ya yi wata magana da ta danganci neman cikin gurbin da Hauwa ta bari ba abinda na lura da shi ma a yanzu ba wannan ne a gabansa ba amma ta fannin abinda ya danganci mu'amula ta aure babu wani abu da ya yi rauni muna shan soyayya launi-launi domin ni dashi gabad'aya mun 'ki bari kanmu ya yi murfi yadda koyaushe yake d'okantuwa da ni haka nima nake kasancewa da shi kamar wata sabuwa dalili ina kasancewa cikin gyara kaina ciki da waje yadda

zai ji dad'i ya kuma yi alfahari dani tare da dakushe masa sha'awar duk wata 'ya mace.

MURFI

Bayan shekaru biyar abubuwa da yawa sun faru masu dadi da marasa dad'i mun yi rashin Hajja haka zalika mun yi rashin Dada mata uku da suka taka muhimmiyar rawa a cikin rayuwarmu  Gwaggo Hajja Dada duka sun amsa kiran Ubangiji suna masu tuba da tabbatar da ya'kini ga Allah. Yadda kowa yake ha'kuri idan ya yi gagarimin rashi haka mu ma duka muka yi hakuri 'ya'ya da jikoki masu aiki da hadimai tare da abokanan arziki. A cikin dai shekarun ne Kamalu ya taka mataki na mussaman fannin addini tauhidi tare da da'awa. Yaro ya yi bazata to amma ba abin mamaki ba ne idan har an yi duba da irin kalubale mabambamta da aka riska tun daga farkon kuruciya har kawo wa yanzu da aka cimma manufa babu shakka addu'ar iyaye tana da tsananin tasiri akan yaransu ba ma su kad'ai takewa tasiri ba har da wad'anda ke abota da su. Na ga zahiri domin ita addu'ar a yanzu na tabbatar da cewar itace take ri'ke da ni har na riski wannan lokacin cikin nutsuwa da hayyacina. Gwani Kamaludden Aminu Salihi a yanzu yana da masters degree (gwani) bayan fafutukar da aka sha wajan neman ilimi littafan addini tun daga kan al'kur'ani mai girma babbbak'u farfaru haddace shi  da kuma rubuce shi. Idan muka zo kan kan litattafan addinin musulunci irinsu fi'kihu ahlari ishmawi iziya risala askari muwad'da malik muddawara kulasatunurulmubin, arba'una hadis, zadizzaujen. Wad'annan littafan addini ne da duk wani mai neman ilimi fannin da'awa ya karance shi Gwani Kamalu ya zauna zaurukan malamai da yawa domin k'arin sani kafin malamansa su bashi izinin zama kan mumbari a katafariyar makarantarsa da uban rik'onsa ya gina da sunansa mai suna *Gwani Kamaludden  tahafizul-kur'an* Ya k'ara da gina massalaci kusa da makarantar domin zaman tafsiri da warware wata mas'alar idan ta taso wadda ta shafi addinin musulunci a k'arshe kuma ya ce ya nemo aure gidan mutunci da tarbiya domin k'ara samun goyon baya da nutsuwar gudanar da  al'amuransa.

To rasuwar Hajja ita ta gyara zazzafar gabar dake tsakanin Inna Uwani da Hajiya Saratu domin dai Inna Uwani  kuka take yi sosai  da Hajiya Saratu a ganinta itace take zuga Hajja ta'ki yafe musu ta zo ta sake zuwa wurin Hajja domin neman gafara da kuka da ro'ko ba a  rabuwar arziki a tsakaninta da Hajiya Saratu domin cikin ikon Allah duk zuwan da za ta yi sai ta risketa a gidan su yi ta babu kyau babu dadi ita Hauwa na can babu wadatacciyar lafiya domin yawan hauhawar jininta ya sanya mata nakasa k'afarta daya ta lanjare da 'kyar take janta a gidan Naziru ma gabad'aya ta zama maririya domin babu wani abinda take iya aiwatarwa tunda babu lafiya kwanciyar aure wannan ba kasafai yake yi da ita ba saboda babu nutsuwar yin kullum cikin ciwo yau da lafiya gobe babu adalci d'aya da ya yi a lamarinta da ya cigaba da zama da ita a hakan bai saketa ba. Ko saukar al'kur'ani da Khalil ya yi Inna Uwani ce kawai ta samu damar zuwa nan abujan tunda ran Hajjan

aka yi wannan bada'kala domin kuwa da kuka ta bar gidan sakamakon irin k'yama da gudun da yaran Hauwa ke yi mata ga Hajiya Saratu ta hana ta motsi a lokacin ne Hajjan ta tsawatar mata tana gaya mata ko bayan ranta bata yarda da wannan matsanaciyar gaba ba babu yadda za a yi da juna tunda an hadu abinda ya riga ya faru sai a bar wa Allah tunda ya wuce yara kuma kada a kuskura a dasa musu kiyayyar uwarsu..

Bayan rasuwar Hajjan ne na ga sun d'an daidaita domin dai mutuwar ta ki'dima mutane da yawa. Har ita Hajiya Saratu ta je can bauchin ta duba Hauwa data na bani labarin halin da take ciki sai da ruwan hawaye ya ciko idona lallai dan adam ba abin komai yake ba Hauwa ta had'u da jarrabawa da kuma ciwo mai tsanani wanda a halin yanzu maigidan ne ke hidima da maganinta mijinta kwabonsa bata ciwon kai ina ma ya ga kudin. Gidansa dai babu yunwa zai kawo ko babu dadi Sadiya ta dafa ta sammata a kwano amma ita da yake Hajiya ce ta fi Hauwan kudi takan yi miyarta ta kaji ko ta namar rago duk ranar dai bai yi cefane Mai kyau ba ta tsakura ta ci ita da yaranta abinda ya kawo shi take bawa Hauwa tunda dai ita kacangal bata iya yi saboda babu isashshiyar lafiya kullum tana dakinta a kwance cikin zullumi da koke koke da wata kafurar nadamar da har ta mutu ba zata musulunta ba.

Zuciyar imani ce ke sanya Sadiya kulawa da ita saboda tana tuna wasu alherai da ta yi mata a lokacin da take da dama a shakarun baya.

Hajiya Saratu da kanta ta zo ta same ni kan cewa idan har Kamalu bai zai tsayar da matar aure ba to sun bashi Aslamiyya jikarta ce ta wurin d'anta na biyu Hafiza ce don kuma tasha wakiltar makarantarsu wurin gasar al'kur'ani k'asashen musulci. Na ce mata ba ni ya kamata ta nema da maganar ba d'an uwanta za ta gayawa tunda dashi suke yi magana ta ce ta sanar da shi kuma ya yi murna sannan ya ce zai tuntubi yaron wannan ha'kkina ne dole a gaya mini. Na ce tunda hakane sai dai kawai na yi fatan alheri da tabbatuwar al'amarin. Dama Salim matarsa yanzu tsohon ciki ne da ita haihuwa ko yau ko gobe ya yi aure shekarar da ta wuce yar gidan abokinsu Alhaji Sulaiman mai suna Suhailat amma ba Hajiya azizaa ce ta haifeta ba matarsa ta biyu ce. Nan gidansu ya gyara wani sashe ya zauna da matarsa amma karfin zamansa yana can legos kusan yanzu shi ya kar'bi ragamar zaman can din shi da Adamu, maigidan ma yakan je idan ta kama amma baya jimawa a can yake dawowa gida k'arfin zaman yanzu yana nan Abuja tunda akwai masu ri'ke masa wata ragamar a can legos din.

Hamusu kuma yana da mata biyu yanzu yaransa hud'u ya sake gina gida mai girma rayuwa ta yi kyau kwarai da gaske babu wanda nake yi wa mugunta kaf cikin yarana na bud'awa kowa ya samu Turzumi ma yana tare da su a kasuwa na ce a sama masa gurbin zama ya fara kasuwanci domin kula da yan uwansa tunda shine namiji babba a gidansu.

Shi kuma Adam idan an yi magana ina budurwarsa sai ya nuna Usaina ta yi ta zum'bura baki tana jin haushi yanzu suna da 16years suna ajin karshe a secondary school. Shekaru biyu da suka wuce suka sauke al'kur'ani mai girma

Minal kuma tana da 14years da yake tana da girman jiki har ta so ta fi su girma da 'barage k'irjinta ma ya fi nasu fitowa uban yana fad'in daga ya

kalleta gabansa yake fad'uwa aure zai yi mata da wuri  idan yana fad'in haka na yi ta dariya yanzu ta yi hankali ta daina wannan rawar kan ta nutsu karatu kawai suka sanya a gaba. Nakan ce duk saurinsa sai ya bari mijin ya fito ya ce ai shi tuntuni ya yi mata miji da na matsananta kuwa Ina fad'in ba da yawuna ba don amanace a hannuna kafin rasuwar Hajja duka yaran sai da ta d'amka mini amanarsu na ce ya bari ba gaggawa ake yi ba don ni ban gaji ba idan har zai dubeta saboda ga'barar jikinta gabansa yana faduwa to ba zai yiwu ya aura mata wanda bata so ba kamar yadda ya tambayi Usaina akan Adamu ta amince tana sonsa itama ya zauna ya tambayeta bud'ar bakinsa ya ce mini ba kowane mijin da ya zab'a mata ba face Yusi. Tun daga lokacin bakina ya mutu ban sake yi masa wata magana ba a duk lokacin da ya tayar da maganar sai na rasa abinda zan ce. Haka kawai ma sai na dawo jin nauyin yarinyar duk da cewa ba ta san wainar da ake toyawa ba sabgarta take yi amma sai na tsinci kaina da 'kin barin mu hada ido a hankali na rage biye mata idan tana yi mini shirme da sangarta abinda ya zame mata jiki a gare ni tun tana yarinya domin da ta tabbatar da cewar Mufida ta 'kwace mata kujerarta wurin Babansu sai ta dawo wajena ni kuma na kar'beta tare da cigaba da lelenta Twins na fad'in su babu mai yinsu a gidan duk lokacin da kishinsu ya tashi. Khalil kuwa yana can Madina karatu makarantar da Kamalu ya yi koyaushe uban na sha'awar Kamalu yana kuma bada misali a kansa da burin Khalil ya yi koyi da shi wajan jajurcewa.
Yusi dama fannin kasuwanci ya karanta don haka tun bayan kammala kararunsa kasuwancinmu ya b'unkasa dalili shine a yanzu ke fita waje yi mana order  dubai chaina India da oman zamansa a najeria yakan zama ta'kaitacce dalilin wannan zurga zurgar shi da Saminu tuni sun kammala gidajensu a rijiyar zaki wajan d'ambare don shi Saminu ma har an kai kud'in aure  da sanya rana. Jikin gidajen da suka gina na sanya su yi mini bhole guda biyu hadiya ga mahaifiyata na kuma gina madaidaitan masallatai uku hubusi duk a gareta Babanmu na bashi za'bi sabon gida ko kuma a sabunta masa wanda yake ciki a yanzu ya ce a sabunta masa gidansa na gado iyaye da kakkani. Gabad'aya aka rushe shi aka yi sabon gini na zamani kowacce aka sanya mata sabbin kayan d'aki. Addu'a muna shanta da ni da shi daga bakuna mabambamta dalilin hannunmu da yake zaga  ko'ina.
Ban san abinda yake tsakanin Abahuraira da Hassana ba katsam Baban Saude ya kira ni a waya yana tambayata menene a tsakaninsu domin kuwa da suka je ganin gida saifullahi ya gaya masa wata magana a kansu.
Na ce da shi ban san komai ba amma ya tambayi Babansu ya ce shikkenan zai neme shi.
A daran kuwa suka yi waya shima dai bai san suna soyayya ba sai da ya kira yarinyar muka titsiyata ta fara kame-kame daga karshe dai ta bada amsar da muke so mu ji daga gare ta tana dariya uban na taya kamar wasu shashashai haka na tsaya ina kallonsu shi da ita idan yana wata shiriritar da yaran ya yi ta ba ni haushi shiyasa gashinan sun mayar dashi kakansu tunda tsakani da Allah a ganina wannan mas'alar ai ta jin kunya ce amma babu ita shi da yarinyar yana tsokanarta tana k'yalkyala dariya.

Ya sanar da Baban Saude ya bawa Abahuraira Hassana a duk lokacin da ya kintsa Baban Saude ya ce a kintse suke son samu a had'a duka dana Kamalu da Usai da Adamu. Wanda za a yi shi bayan dawowarmu daga aikin hajji kamar yadda suka tsayar da lokaci. Wanda ya yi daidai da lokacin da za su kammala secondary  amma da shara'din barinsu cigaba da karatu koda an yi auran

Suka tsayar da magana a haka bayan wasu kwanaki kuma yake gaya mini za a had'a da Minal kawai duk da ajinta biyar ita yanzu na ce a a ba za a tsinke mata karatu ba bayan haka kuma ba ta yi k'warinsu ba, sannan kuma shi yake sabgarsa shi kad'ai babu wanda ya gayawa a cikin yaran balle su san halin da ake ciki ba a yin haka. Ya ce ya gayawa Yusi a waya kuma ya amince.  Na ce to itama a gaya mata ya dinga dawurwura alamu sun nuna yana jin tsoron rigimarta abin mamaki ko da ya gaya mata ya yi mata miji da farko zum'bura baki ta dinga yi da k'ananun hawaye amma yana gaya mata wanda ya zab'a mata ta sinne kanta tana murmushi nan ma ya dinga kyakyata dariya kamar wani sabon kamu abin ya dinga ba ni haushi da mamaki. Ta tashi ta sauka 'kasa da sauri yadda ta nuna alamu ta amshi tayin da aka yi mata kuma Yusi ya samu gurbi a cikin zuciyarta.
A wannan shekaran rabon kujerar hajji ya yi anti Yagana da Ya Falmata sun rabauta da ta su. Baban Saude da kuma babamu suma sun samu tasu. Sai iyalinsa gabad'aya ni da shi da yaranmu har da Mufida da kuma Adam da Sukairaju muka d'unguma zuwa kasa mai tsarki domin yin aikin Hajji. Masu aiki muka bari a gidan.  A can muka riski Khalil kamar yadda muke hasashe ya yi wata iriyar kamala ta ban mamaki kamar dai yadda Kamalu ya yi dama yaro ne mai son girma da manyance sai abinda ya k'aru balle yanzu da ilimin addini ya fara huda shi tare da shi muka yi Hajjin  ya d'auki Mufida ya sa a kafad'arsa sosai na tsananta da ro'ko da addu'a akan Allah Ya tabbatar da alheri bisa wannan had'aka ta auratayya da za mu yi wa yaranmu addu'ata gabad'aya ta ta'allaka ne akan hakan tare da fatan cikawa da imani da kuma samun zuri'ar da duniya za ta yi alfahari da ita......✍
*ALHAMDULILLAHI!*
*ALHAMDULILLAHI*
*ALHAMDULILLAHI!*

Lefin dad'i k'arewa ga dai yadda 'karshen wannan labari ya zo. Ina ro'kon Ubangiji Allah Ya yafe mini abinda na rubuta bisa kuskure wanda na rubuta daidai kuma ina ro'kansa da ya ba ni lada tare da wad'anda suka bibiyeni. Godiyata bata da iyaka akan masoyana na gode na sake godewa wad'anda nasa ni da wad'anda ban sani ba. Comments section na gudun aure lallai kun yi bajinta kuma kun kara mini kwarin gwiwa wajan ganin na isar da sa'kon dana d'auko ba tare da na gaza ba. Na sake fadi kun yi bajinta k'warai ban cire kowa ba. Masu k'orafi kuma ban ji komai ba wannan ma cikin kulawa ne Allah Ya saka da alheri. Za mu cigaba da zumunci da gaisawa cikin comments section kafin zuwan sabon littafi idan Allah Ya sa muna raye. Ina fatan wanda zai zo anan gaba ya fiye muku wannan da muka kammala dad'i

da wa'azantarwa. A yi bikin sallah lafiya aka kuma yi mini tallah a gruops na kammala a arewapen  ga masu jiran karanta complete din littafin....
ALLAH YA SADA MU DA ALHERI.
*GARKUWAR MATA.*
*BINTA UMAR ABBALE*